NOOR
International

ALKUR'ANI MAI GIRMA

V.01

Fihirisa

FATIHA 01
BAKARA 02
ALI-IMRAN 50
NISA'I 77
MA'IDA 106
AN'AM 128
A'ARAF 151
ANFAL 177
TAUBA 187
YUNUS 208
HUD 221
YUSUF 235
RA'AD 249
IBRAHIM 255
HIJR 262
NAHL 267
ISRA'I 282
KAHF 293
MARYAM 305
DA HA 312
ANBIYA 322
HAJJI 332

Fihirisa

MU'UMINUN 342
NUR..... 350
FURKAN..... 359
SHU'ARA..... 367
NAMLI 377
KASAS 385
ANKABUT 396
RUM 404
LUKMAN..... 411
SAJDA 415
AHZAB..... 418
SABA'I 428
FADIR 434
YASIN..... 440
SAFFAT 446
SAD..... 453
ZUMAR..... 458
GHAFIR..... 467
FUSSILAT..... 477
SHURA 483
ZUKHRUF 489
DUKHAN..... 496

Fihirisa

JASIYA..... 499
AHKAF 502
MUHAMMAD 507
FAT'H 511
HUJURAT 515
KAF..... 518
ZARIYAT 520
DUR 523
NAJM 526
KAMAR..... 528
RAHMAN..... 531
WAKI'A 534
HADID 537
MUJADILA 542
HASHR..... 545
MUMTAHANA..... 549
SAFF 551
JUMU'A..... 553
MUNAFIKUN 554
TAGHABUN..... 556
DALAK 558
TAHRIM..... 560

Fihirisa

MULK..... 562
KALAM..... 564
HAKKA 566
MA'ARIJ 568
NUH..... 570
JINN 572
MUZZAMMIL 574
MUDDASSIR 575
KIYAMA 577
INSAN 578
MURSALAT 580
NABA'I 582
NAZI'AT 583
ABASA 585
TAKWIR..... 586
INFIDAR 587
MUDAFFIFIN 587
INSHIKAK..... 589
BURUJ..... 590
DARIK..... 591
A'ALA..... 591
GHASHIYA..... 592

Fihirisa

FAJR 593
BALAD 594
SHAMS 595
LAIL 595
DHUHA 596
SHARH 596
TIN 597
ALAK 597
KADAR 598
BAYYINA 598
ZALZALA 599
ADIYAT 599
KARI'A 600
TAKASUR 600
ASR 601
HUMAZA 601
FIL 601
KURAISH 602
MA'UN 602
KAUSAR 602
KAFIRUN 603
NASR 603

Fihirisa

MASAD 603

IKHLAS..... 604

FALAK 604

NAS 604

Sura Fatiha



(1) Da sunan Allah Mai Rahama Mai Jin ƙai[1]

(2) Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin talikai

(3) Mai rahama Mai jin ƙai[2]

(4) Mamallakin ranar sakamako

(5) Kai kaɗai muke bautata wa, kuma Kai kaɗai muke neman taimakonka

(6) Ka shiryar da mu tafarkin nan madaidaici

(7) Tafarkin waɗanda Ka yi wa ni'ima[3] , ba waɗanda aka yi fushi da su ba[4] , ba kuma ɓatattu ba[5]

(1) Bisimilla Alƙur'ani ce, kuma aya ce a 'Suratun Namli aya ta 30'; sannan ita aya ce a farkon 'Suratul Fatiha', sannan an saukar da ita a farkon kowace sura don bambance tsakanin ƙarshen sura da farkon wata sura. Amma ban da tsakanin 'Suratul Anfal' da 'Taubah'.

(2) Allah, suna ne na wanda ya cancanta a bauta masa shi kaɗai. Ba a kiran wani da shi. Arrahman wanda yake nuna yalwatacciyar rahmar Allah wadda take shafar kowa da komai a nan duniya da kuma sunansa Arrahim, wanda yake nuna keɓantacciyar rahamarsa a lahira ga muminai kawai masu tsoran sa.

(3) Su ne waɗanda aka ambata a aya ta 69 a Suratun Nisa'i.

(4) Watau waɗanda suka san gaskiya suka take, kamar Yahudawa.

(5) Watau waɗanda suke bautar Allah da jahilci, kamar Nasara.

Sura Baƙara



(1) ALIF LAM MIM[1]

(2) Wannan littafin babu wani kokwanto a cikinsa; shiriya ne ga masu taƙawa[2]

(3) Waɗanda suke yin imani da gaibi kuma suke tsayar da salla kuma suke ciyarwa daga abin da Muka arzuta su da shi

(4) Waɗanda suke yin imani da abin da aka saukar maka da abin da aka saukar a gabaninka, kuma suke sakankancewa da ranar lahira

(5) Waɗannan suna kan (babbar) shiriya daga Ubangijinsu, kuma waɗannan su ne masu samun babban rabo

(1) Allah ( ) ya buɗe wannan Sura da harufan Alif da Lam da Mim. Hakanan akwai surorin da dama da Allah ya buɗe su da irin waɗannan datsattsun haruffa. Allah ne kaɗai ya san haƙiƙanin abin da yake nufi da su. Wasu malamai na cewa, Allah yana nuna mu'ujizar Alƙurani ne da irin waɗannan haruffa.

(2) Taƙawa tana nufin aikata abin Allah ya wajabta da nisantar abin da ya haramta.

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ سَوَآءٌ عَلَيْهِمْ ءَأَنذَرْتَهُمْ أَمْ لَمْ تُنذِرْهُمْ
لَا يُؤْمِنُونَ ﴿٦﴾ خَتَمَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ وَعَلَىٰ سَمْعِهِمْ ۖ وَعَلَىٰٓ
أَبْصَٰرِهِمْ غِشَٰوَةٌ ۖ وَلَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿٧﴾ وَمِنَ ٱلنَّاسِ
مَن يَقُولُ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَبِٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَمَا هُم بِمُؤْمِنِينَ ﴿٨﴾
يُخَٰدِعُونَ ٱللَّهَ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَمَا يَخْدَعُونَ إِلَّآ أَنفُسَهُمْ
وَمَا يَشْعُرُونَ ﴿٩﴾ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ فَزَادَهُمُ ٱللَّهُ مَرَضًا ۖ
وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌۢ بِمَا كَانُوا۟ يَكْذِبُونَ ﴿١٠﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ
لَا تُفْسِدُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ قَالُوٓا۟ إِنَّمَا نَحْنُ مُصْلِحُونَ ﴿١١﴾ أَلَآ إِنَّهُمْ
هُمُ ٱلْمُفْسِدُونَ وَلَٰكِن لَّا يَشْعُرُونَ ﴿١٢﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ
ءَامِنُوا۟ كَمَآ ءَامَنَ ٱلنَّاسُ قَالُوٓا۟ أَنُؤْمِنُ كَمَآ ءَامَنَ ٱلسُّفَهَآءُ ۗ
أَلَآ إِنَّهُمْ هُمُ ٱلسُّفَهَآءُ وَلَٰكِن لَّا يَعْلَمُونَ ﴿١٣﴾ وَإِذَا لَقُوا۟
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ قَالُوٓا۟ ءَامَنَّا وَإِذَا خَلَوْا۟ إِلَىٰ شَيَٰطِينِهِمْ قَالُوٓا۟ إِنَّا
مَعَكُمْ إِنَّمَا نَحْنُ مُسْتَهْزِءُونَ ﴿١٤﴾ ٱللَّهُ يَسْتَهْزِئُ بِهِمْ وَيَمُدُّهُمْ
فِى طُغْيَٰنِهِمْ يَعْمَهُونَ ﴿١٥﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱشْتَرَوُا۟ ٱلضَّلَٰلَةَ
بِٱلْهُدَىٰ فَمَا رَبِحَت تِّجَٰرَتُهُمْ وَمَا كَانُوا۟ مُهْتَدِينَ ﴿١٦﴾

(6) Lalle waɗanda suka kafirta, duk ɗaya ne a gare su, ka yi musu gargaɗi ko ba ka yi musu ba, ba za su yi imani ba
(7) Allah Ya toshe zukatansu da jinsu, kuma akwai wani lullubi a kan idanunsu, kuma suna da azaba mai girma
(8) A cikin mutane kuma akwai waɗanda suke cewa: "Mun yi imani da Allah kuma mun yi imani da ranar lahira," alhalin su ba muminai ne ba
(9) Suna ganin suna yaudarar Allah ne da waɗanda suka yi imani, amma kuwa ba kowa suke yaudara ba sai kawunansu, kuma su ba sa jin hakan

(10) Akwai wata cuta (ta munafunci) a cikin zukatansu, sai Allah Ya ƙara musu wata cutar, kuma suna da wata azaba mai raɗaɗi saboda ƙaryar da suke yi
(11) Idan kuma aka ce musu: "Kada ku yi ɓarna a bayan ƙasa", sai su ce: "Mu fa masu gyara ne kawai."
(12) Saurara, lalle su su ne maɓarnata, amma ba sa jin hakan
(13) Idan kuma aka ce da su: "Ku yi imani kamar yadda mutane suka yi imani", sai su ce: "Shin za mu yi imani ne kamar yadda wawaye suka yi imani?" Saurara, lalle su ne wawayen, sai dai ba sa sanin (hakan)
(14) Idan kuma suka haɗu da waɗanda suka yi imani sai su ce: "Mun yi imani." To amma idan suka keɓanta da shaiɗanunsu (iyayen gidansu)[1] sai su ce: "Mu fa lalle muna nan tare da ku, mu kawai izgili ne muke yi."
(15) Allah Yana yi musu izgili, kuma Yana yi musu talala cikin shisshiginsu suna masu ɗimuwa
(16) Waɗannan su ne suka musanya shiriya da ɓata, don haka kasuwancinsu bai yi riba ba, kuma ba su zamo shiryayyu ba

(1) Shedanunsu, su ne manyan kafirai da Yahudawa.

مَثَلُهُمْ كَمَثَلِ ٱلَّذِى ٱسْتَوْقَدَ نَارًا فَلَمَّآ أَضَآءَتْ مَا حَوْلَهُۥ
ذَهَبَ ٱللَّهُ بِنُورِهِمْ وَتَرَكَهُمْ فِى ظُلُمَٰتٍ لَّا يُبْصِرُونَ ﴿١٧﴾ صُمٌّۢ
بُكْمٌ عُمْىٌ فَهُمْ لَا يَرْجِعُونَ ﴿١٨﴾ أَوْ كَصَيِّبٍ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ فِيهِ
ظُلُمَٰتٌ وَرَعْدٌ وَبَرْقٌ يَجْعَلُونَ أَصَٰبِعَهُمْ فِىٓ ءَاذَانِهِم مِّنَ
ٱلصَّوَٰعِقِ حَذَرَ ٱلْمَوْتِ ۚ وَٱللَّهُ مُحِيطٌۢ بِٱلْكَٰفِرِينَ ﴿١٩﴾ يَكَادُ ٱلْبَرْقُ
يَخْطَفُ أَبْصَٰرَهُمْ ۖ كُلَّمَآ أَضَآءَ لَهُم مَّشَوْا۟ فِيهِ وَإِذَآ أَظْلَمَ عَلَيْهِمْ
قَامُوا۟ ۚ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ لَذَهَبَ بِسَمْعِهِمْ وَأَبْصَٰرِهِمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ
كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٢٠﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعْبُدُوا۟ رَبَّكُمُ ٱلَّذِى
خَلَقَكُمْ وَٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿٢١﴾ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ
ٱلْأَرْضَ فِرَٰشًا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءً وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجَ
بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزْقًا لَّكُمْ ۖ فَلَا تَجْعَلُوا۟ لِلَّهِ أَندَادًا وَأَنتُمْ
تَعْلَمُونَ ﴿٢٢﴾ وَإِن كُنتُمْ فِى رَيْبٍ مِّمَّا نَزَّلْنَا عَلَىٰ عَبْدِنَا فَأْتُوا۟
بِسُورَةٍ مِّن مِّثْلِهِۦ وَٱدْعُوا۟ شُهَدَآءَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ إِن
كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٢٣﴾ فَإِن لَّمْ تَفْعَلُوا۟ وَلَن تَفْعَلُوا۟ فَٱتَّقُوا۟ ٱلنَّارَ
ٱلَّتِى وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلْحِجَارَةُ ۖ أُعِدَّتْ لِلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٤﴾

(17) Misalinsu kamar misalin wanda ya wahala har ya kunna wuta ne, yayin da ta haskaka abin da yake daura da shi, sai Allah Ya tafiyar da haskensu Ya bar su cikin duffai ba sa gani

(18) (Su) kurame ne, bebaye ne, makafi ne, don haka ba za su taɓa dawowa (kan gaskiya) ba

(19) Ko kuma (misalinsu) kamar wani mamakon ruwan sama ne, wanda yake ɗauke da duffai da tsawa da walƙiya, har ta kai suna sanya ‘yan yatsunsu cikin kunnuwansu don tsananin tsawarwaki saboda tsoron mutuwa. Allah Kuma Yana kewaye da kafirai (da iliminsa)

(20) Walƙiyar ta kusa ta fauce idanuwansu. Duk sa›adda ta haska musu sai su ci gaba da tafiya cikin (haskenta); idan kuma ta rufe su da duhu sai su tsaya cak. Da kuwa Allah Ya ga dama da sai Ya tafiyar da jinsu da ganinsu. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai

(21) Ya ku mutane, ku bauta wa Ubangijinku Wanda Ya halicce ku, da waɗanda suka gabace ku, don ku samu taƙawa

(22) Shi ne Wanda Ya sanya muku ƙasa ta zama shimfiɗa kuma Ya sanya muku sama ta zama gini kuma Ya saukar da ruwa daga sama Ya fitar muku da arziƙi na ‘ya’yan itatuwa, don haka kada ku sanya wa Allah kishiyoyi alhalin kuna sane

23) Kuma idan kun kasance cikin kokwanto game da abin da Muka saukar wa bawanmu, to ku zo da kwatankwacin sura ɗaya kamarsa, kuma ku kirawo masu taimakonku ba Allah ba in kun kasance masu gaskiya

(24) To idan har ba ku aikata hakan ba, kuma ba za ku taɓa iyawa ba, to ku kiyayi wata wuta wadda mutane ne da duwatsu makamashinta; an kuwa tanade ta domin kafirai

وَبَشِّرِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أَنَّ لَهُمۡ جَنَّٰتٖ
تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ كُلَّمَا رُزِقُواْ مِنۡهَا مِن ثَمَرَةٖ
رِّزۡقٗا قَالُواْ هَٰذَا ٱلَّذِي رُزِقۡنَا مِن قَبۡلُۖ وَأُتُواْ بِهِۦ مُتَشَٰبِهٗاۖ
وَلَهُمۡ فِيهَآ أَزۡوَٰجٞ مُّطَهَّرَةٞۖ وَهُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٢٥ إِنَّ
ٱللَّهَ لَا يَسۡتَحۡيِۦٓ أَن يَضۡرِبَ مَثَلٗا مَّا بَعُوضَةٗ فَمَا فَوۡقَهَاۚ فَأَمَّا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فَيَعۡلَمُونَ أَنَّهُ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّهِمۡۖ وَأَمَّا
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَيَقُولُونَ مَاذَآ أَرَادَ ٱللَّهُ بِهَٰذَا مَثَلٗاۘ
يُضِلُّ بِهِۦ كَثِيرٗا وَيَهۡدِي بِهِۦ كَثِيرٗاۚ وَمَا يُضِلُّ بِهِۦٓ
إِلَّا ٱلۡفَٰسِقِينَ ٢٦ ٱلَّذِينَ يَنقُضُونَ عَهۡدَ ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ
مِيثَٰقِهِۦ وَيَقۡطَعُونَ مَآ أَمَرَ ٱللَّهُ بِهِۦٓ أَن يُوصَلَ وَيُفۡسِدُونَ
فِي ٱلۡأَرۡضِۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٢٧ كَيۡفَ
تَكۡفُرُونَ بِٱللَّهِ وَكُنتُمۡ أَمۡوَٰتٗا فَأَحۡيَاكُمۡۖ ثُمَّ يُمِيتُكُمۡ
ثُمَّ يُحۡيِيكُمۡ ثُمَّ إِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٢٨ هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَ
لَكُم مَّا فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰٓ إِلَى ٱلسَّمَآءِ
فَسَوَّىٰهُنَّ سَبۡعَ سَمَٰوَٰتٖۚ وَهُوَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ٢٩

(25) Kuma ka yi albishir ga waɗanda suka yi imani kuma suka aikata ayyuka na ƙwarai cewa suna da wasu gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Duk sa'adda aka arzuta su da 'ya'yan itatuwa daga gare su sai su ce: "Wannan shi ne irin abin da aka arzuta mu da shi ɗazu." An kawo musu shi yana mai kama da juna, kuma suna da wasu mata tsarkaka a cikinsu, kuma su masu zama ne a cikinsu dindindin

(26) Lalle Allah ba Ya jin kunyar buga kowanne irin misali komai ƙanƙantarsa, sauro da abin da ya fi shi. To amma waɗanda suka yi imani suna sanin cewa, lalle shi (wannan misali) gaskiya ne daga Ubangijinsu. Amma waɗanda suka kafirta sai su riƙa cewa: "Me Allah Yake nufi da wannan misalin?" Yana kuwa ɓatar da mutane da yawa da shi, kuma Ya shiryar da mutane da yawa da shi, kuma ba kowa Yake ɓatarwa da shi ba sai fasiƙai

(27) Waɗanda suke warware alƙawarin Allah bayan ƙulla shi, kuma suke yanke abin da Allah Ya yi umarni a sadar da shi, kuma suke ɓarna a bayan ƙasa. Waɗannan su ne cikakkun hasararru

(28) Ta yaya kuke kafirce wa Allah alhalin a da kun kasance matattu, sannan Ya raya ku, sannan zai kuma mayar da ku matattu sannan Ya raya ku (a karo na biyu) sannan zuwa gare Shi ake mayar da ku?

(29) Shi ne wanda Ya halitta muku abin da yake cikin ƙasa gaba ɗaya, sannan Ya nufi sama Ya daidaita su sammai bakwai, kuma Shi Masanin komai ne

وَإِذْ قَالَ رَبُّكَ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ إِنِّي جَاعِلٌ فِي ٱلْأَرْضِ خَلِيفَةً ۖ قَالُوٓا۟
أَتَجْعَلُ فِيهَا مَن يُفْسِدُ فِيهَا وَيَسْفِكُ ٱلدِّمَآءَ وَنَحْنُ نُسَبِّحُ
بِحَمْدِكَ وَنُقَدِّسُ لَكَ ۖ قَالَ إِنِّيٓ أَعْلَمُ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿٣٠﴾ وَعَلَّمَ
ءَادَمَ ٱلْأَسْمَآءَ كُلَّهَا ثُمَّ عَرَضَهُمْ عَلَى ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ فَقَالَ
أَنۢبِـُٔونِى بِأَسْمَآءِ هَٰٓؤُلَآءِ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٣١﴾ قَالُوا۟ سُبْحَٰنَكَ
لَا عِلْمَ لَنَآ إِلَّا مَا عَلَّمْتَنَآ ۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٣٢﴾ قَالَ يَٰٓـَٔادَمُ
أَنۢبِئْهُم بِأَسْمَآئِهِمْ ۖ فَلَمَّآ أَنۢبَأَهُم بِأَسْمَآئِهِمْ قَالَ أَلَمْ أَقُل
لَّكُمْ إِنِّيٓ أَعْلَمُ غَيْبَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَأَعْلَمُ مَا تُبْدُونَ
وَمَا كُنتُمْ تَكْتُمُونَ ﴿٣٣﴾ وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ ٱسْجُدُوا۟ لِـَٔادَمَ
فَسَجَدُوٓا۟ إِلَّآ إِبْلِيسَ أَبَىٰ وَٱسْتَكْبَرَ وَكَانَ مِنَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٣٤﴾ وَقُلْنَا
يَٰٓـَٔادَمُ ٱسْكُنْ أَنتَ وَزَوْجُكَ ٱلْجَنَّةَ وَكُلَا مِنْهَا رَغَدًا حَيْثُ
شِئْتُمَا وَلَا تَقْرَبَا هَٰذِهِ ٱلشَّجَرَةَ فَتَكُونَا مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٣٥﴾ فَأَزَلَّهُمَا
ٱلشَّيْطَٰنُ عَنْهَا فَأَخْرَجَهُمَا مِمَّا كَانَا فِيهِ ۖ وَقُلْنَا ٱهْبِطُوا۟ بَعْضُكُمْ
لِبَعْضٍ عَدُوٌّ ۖ وَلَكُمْ فِى ٱلْأَرْضِ مُسْتَقَرٌّ وَمَتَٰعٌ إِلَىٰ حِينٍ ﴿٣٦﴾ فَتَلَقَّىٰٓ
ءَادَمُ مِن رَّبِّهِۦ كَلِمَٰتٍ فَتَابَ عَلَيْهِ ۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٣٧﴾

(30) Kuma ka tuna sa'adda Ubangijinka Ya ce da mala'iku: "Lalle ni zan sanya wani halifa[1] a bayan ƙasa." Suka ce: "Yanzu za Ka sanya mata wanda zai yi ɓarna a cikinta kuma ya zubar da jini, alhali ga mu muna tasbihi tare da gode Maka, kuma muna tsarkake Ka?" (Allah) Ya ce: "Ni fa tabbas Na san abin da ku ba ku sani ba."

(31) Kuma sai (Allah) Ya koya wa Adamu dukkan sunaye (na abubuwa) sannan Ya kawo su gaban mala'iku, sai Ya ce: "Ku faɗa min sunayen waɗannan abubuwan in kun zamanto masu gaskiya."

(32) Sai suka ce: "Tsarki ya tabbata a gare Ka, ba mu da wani ilimi sai wanda Ka sanar da mu. Lalle Kai ne cikakken Masani, Mai hikima."

(33) Ya ce: "Ya Adamu faɗa musu sunayensu." Yayin da ya faɗa musu sunayensu, sai (Allah) Ya ce: "Ba Na faɗa muku cewa, lalle Ni ne Nake sane da gaibin sammai da ƙasa ba, kuma Nake sane da abin da kuke bayyanawa da kuma abin da kuke ɓoyewa ba?"

(34) Kuma ka tuna lokacin da Muka ce wa mala'iku: "Ku yi sujjada ga Adamu." Sai duk suka yi sujjada[2], in ban da Iblis, sai shi ya ƙi, ya kuma yi girman kai, kuma ya tabbata cikin kafirai

(35) Kuma Muka ce: "Ya kai Adamu, ka zauna gidan Aljanna kai da matarka, kuma ku ci (kayan marmarinta) cikin yalwa a duk inda kuka ga dama, kada kuma ku kuskura ku kusanci wannan bishiyar, sai ku kasance daga cikin azzalumai."

(36) Sai Shaiɗan ya zamar da su[3] game da ita (bishiyar), sai ya fitar da su daga ni'imar da suke ciki. Sai Muka ce: "Ku sauko ƙasa sashinku yana mai gaba da sashi; kuma kuna da mazauni a bayan ƙasa da wani jin daɗi zuwa wani ɗan lokaci."

(37) Sai Adamu ya karɓi wasu kalmomi daga Ubangijinsa (na neman gafara), sai Ya yafe masa; lalle Shi ne Mai yawan karɓar tuba kuma Mai yawan jin ƙai

(1) Halifa, shi ne Annabi Adamu ( ) da zuriyarsa, waɗanda za su riƙa maye gurbin juna a bayan ƙasa.

(2) Mala'iku sun yi wa Adamu ( ) sujjada ne don biyayya ga umarnin Allah. Ba ya halatta a Musulunci wani ya yi wa wani sujjada ba Allah ba.ipsum

(3) Ta hanyar yi musu waswasi, kamar yadda ya zo a Suratul A'raf, aya ta 20, da Ɗaha, aya ta 120.

قُلْنَا ٱهْبِطُوا۟ مِنْهَا جَمِيعًا ۖ فَإِمَّا يَأْتِيَنَّكُم مِّنِّى هُدًى فَمَن تَبِعَ
هُدَاىَ فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٣٨﴾ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟
وَكَذَّبُوا۟ بِـَٔايَـٰتِنَآ أُو۟لَـٰٓئِكَ أَصْحَـٰبُ ٱلنَّارِ ۖ هُمْ فِيهَا خَـٰلِدُونَ ﴿٣٩﴾
يَـٰبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ٱذْكُرُوا۟ نِعْمَتِىَ ٱلَّتِىٓ أَنْعَمْتُ عَلَيْكُمْ وَأَوْفُوا۟ بِعَهْدِىٓ
أُوفِ بِعَهْدِكُمْ وَإِيَّـٰىَ فَٱرْهَبُونِ ﴿٤٠﴾ وَءَامِنُوا۟ بِمَآ أَنزَلْتُ مُصَدِّقًا
لِّمَا مَعَكُمْ وَلَا تَكُونُوٓا۟ أَوَّلَ كَافِرٍۭ بِهِۦ ۖ وَلَا تَشْتَرُوا۟ بِـَٔايَـٰتِى
ثَمَنًا قَلِيلًا وَإِيَّـٰىَ فَٱتَّقُونِ ﴿٤١﴾ وَلَا تَلْبِسُوا۟ ٱلْحَقَّ بِٱلْبَـٰطِلِ وَتَكْتُمُوا۟
ٱلْحَقَّ وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٤٢﴾ وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ
وَٱرْكَعُوا۟ مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ ﴿٤٣﴾ أَتَأْمُرُونَ ٱلنَّاسَ بِٱلْبِرِّ
وَتَنسَوْنَ أَنفُسَكُمْ وَأَنتُمْ تَتْلُونَ ٱلْكِتَـٰبَ ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿٤٤﴾
وَٱسْتَعِينُوا۟ بِٱلصَّبْرِ وَٱلصَّلَوٰةِ ۚ وَإِنَّهَا لَكَبِيرَةٌ إِلَّا عَلَى ٱلْخَـٰشِعِينَ
﴿٤٥﴾ ٱلَّذِينَ يَظُنُّونَ أَنَّهُم مُّلَـٰقُوا۟ رَبِّهِمْ وَأَنَّهُمْ إِلَيْهِ رَٰجِعُونَ ﴿٤٦﴾
يَـٰبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ٱذْكُرُوا۟ نِعْمَتِىَ ٱلَّتِىٓ أَنْعَمْتُ عَلَيْكُمْ وَأَنِّى فَضَّلْتُكُمْ
عَلَى ٱلْعَـٰلَمِينَ ﴿٤٧﴾ وَٱتَّقُوا۟ يَوْمًا لَّا تَجْزِى نَفْسٌ عَن نَّفْسٍ شَيْـًٔا
وَلَا يُقْبَلُ مِنْهَا شَفَـٰعَةٌ وَلَا يُؤْخَذُ مِنْهَا عَدْلٌ وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿٤٨﴾

(38) Muka ce: “Dukkanku ku sauko daga cikinta, sannan idan wata shiriyata ta zo muku, to wadanda suka bi shiriyata, babu wani tsoro a tare da su, kuma ba za su yi bakin ciki ba

(39) Kuma wadanda suka kafirta suka kuma karyata ayoyinmu, wadannan su ne ‘yan wuta, su masu dawwama ne a cikinta

(40) Ya ku ‘ya’yan Isra’ila, ku tuna ni’imata da Na yi muku, kuma ku cika alkawarina zan cika muku alkawarinku, kuma ku tsorace Ni Ni kadai

(41) Kuma ku yi imani da abin da Na saukar yana mai gaskata abin da yake tare da ku (na wahayi), kada kuma ku zama farkon (jinsinku) da zai kafirce masa, kuma kada ku sayar da ayoyina da dan kudi kadan, kuma ku kiyaye dokokina

(42) Kada kuma ku gauraya gaskiya da karya, kuma ku boye gaskiya, alhalin kuna sane

(43) Kuma ku tsayar da salla, ku kuma ba da zakka, kuma ku yi ruku’i tare da masu ruku’i

(44) Shin yanzu kwa rika umartar mutane da ayyukan alheri ku kuma kuna mantawa da kawunanku, alhalin kuna karanta Littafi? Ashe ba za ku hankalta ba?

(45) Kuma ku nemi agaji ta hanyar hakuri da kuma salla, kuma lalle ita (salla) babban abu ne sai dai ga masu kaskantar da kai

(46) Wadanda suka tabbatar da cewa, su masu haduwa ne da Ubangijinsu, kuma su zuwa gare Shi suke komawa

(47) Ya ku ‘ya’yan Isra’ila ku tuna ni’imata da Na yi muku, kuma Ni Na fifita ku a kan sauran mutanen duniya (na zamaninku)

(48) Kuma ku kiyayi wata rana da babu wani (mai) rai da zai isar wa da wani (mai) rai komai a cikinta; kuma ba za a karbi wani ceto daga gare shi ba, kuma ba za a karbi wata fansa daga gare shi ba, kuma ba za a taimaka musu ba

وَإِذْ نَجَّيْنَٰكُم مِّنْ ءَالِ فِرْعَوْنَ يَسُومُونَكُمْ سُوٓءَ ٱلْعَذَابِ
يُذَبِّحُونَ أَبْنَآءَكُمْ وَيَسْتَحْيُونَ نِسَآءَكُمْ ۚ وَفِى ذَٰلِكُم بَلَآءٌ
مِّن رَّبِّكُمْ عَظِيمٌ ﴿٤٩﴾ وَإِذْ فَرَقْنَا بِكُمُ ٱلْبَحْرَ فَأَنجَيْنَٰكُمْ
وَأَغْرَقْنَآ ءَالَ فِرْعَوْنَ وَأَنتُمْ تَنظُرُونَ ﴿٥٠﴾ وَإِذْ وَٰعَدْنَا مُوسَىٰٓ
أَرْبَعِينَ لَيْلَةً ثُمَّ ٱتَّخَذْتُمُ ٱلْعِجْلَ مِنۢ بَعْدِهِۦ وَأَنتُمْ ظَٰلِمُونَ
﴿٥١﴾ ثُمَّ عَفَوْنَا عَنكُم مِّنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿٥٢﴾
وَإِذْ ءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْفُرْقَانَ لَعَلَّكُمْ تَهْتَدُونَ ﴿٥٣﴾
وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦ يَٰقَوْمِ إِنَّكُمْ ظَلَمْتُمْ أَنفُسَكُم بِٱتِّخَاذِكُمُ
ٱلْعِجْلَ فَتُوبُوٓا۟ إِلَىٰ بَارِئِكُمْ فَٱقْتُلُوٓا۟ أَنفُسَكُمْ ذَٰلِكُمْ
خَيْرٌ لَّكُمْ عِندَ بَارِئِكُمْ فَتَابَ عَلَيْكُمْ ۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلتَّوَّابُ
ٱلرَّحِيمُ ﴿٥٤﴾ وَإِذْ قُلْتُمْ يَٰمُوسَىٰ لَن نُّؤْمِنَ لَكَ حَتَّىٰ نَرَى ٱللَّهَ
جَهْرَةً فَأَخَذَتْكُمُ ٱلصَّٰعِقَةُ وَأَنتُمْ تَنظُرُونَ ﴿٥٥﴾ ثُمَّ بَعَثْنَٰكُم
مِّنۢ بَعْدِ مَوْتِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿٥٦﴾ وَظَلَّلْنَا عَلَيْكُمُ
ٱلْغَمَامَ وَأَنزَلْنَا عَلَيْكُمُ ٱلْمَنَّ وَٱلسَّلْوَىٰ ۖ كُلُوا۟ مِن طَيِّبَٰتِ
مَا رَزَقْنَٰكُمْ ۚ وَمَا ظَلَمُونَا وَلَٰكِن كَانُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿٥٧﴾

(49) Kuma ku tuna lokacin da Muka kuɓutar da ku daga jama'ar Fir'auna waɗanda suke ɗanɗana muku mummunar azaba, suna yanka 'ya'yanku maza, kuma suna ƙyale 'ya'yanku mata. A cikin wannan lamari akwai babbar jarraba daga Ubangijinku

(50) Kuma ku tuna lokacin da Muka raba muku kogi, sai Muka kuɓutar da ku, kuma Muka nutsar da jama'ar Fir'auna, alhalin kuna kallo

(51) Kuma ku tuna lokacin da Muka yi wa Musa wa'adin (ganawa da shi) na kwana arba'in, sannan ku kuma kuka kama bautar ɗan maraƙi a bayansa, alhalin kuna masu zaluntar kawunanku

(52) Sannan sai Muka yi muku afuwa bayan haka, don ku yi godiya

(53) Kuma ku tuna lokacin da Muka ba wa Musa Littafin (Attaura) da abin da yake rarrabewa (tsakanin gaskiya da ƙarya) don ku shiriya

(54) Kuma ku tuna lokacin da Musa ya cewa mutanensa: "Ya ku mutanena, lalle ku kun zalunci kawunanku ta hanyar mayar da ɗan maraƙi abin bauta, don haka ku tuba zuwa ga Mahaliccinku, kuma ku kashe kawunanku; wannan shi ne ya fi alheri a gare ku a wajen Mahaliccinku. Lalle shi Mai yawan karɓar tuba ne, Mai yawan jin ƙai."

(55) Kuma ku tuna lokacin da kuka ce: "Ya Musa ba za mu yi imani da kai ba har sai mun ga Allah a sarari", sai tsawa ta halaka ku, alhali kuma kuna kallo

(56) Sannan sai Muka tashe ku bayan mutuwarku, don ku yi godiya

(57) Kuma Muka yi muku inuwa da girgije, kuma Muka saukar muku da mannu da (soyayyun) tsuntsayen salwa, ku ci daga daɗaɗan abin da Muka arzuta ku da shi; kuma ba su zalince Mu ba, sai dai kawunansu kaɗai suke zalunta

وَإِذْ قُلْنَا ٱدْخُلُوا۟ هَٰذِهِ ٱلْقَرْيَةَ فَكُلُوا۟ مِنْهَا حَيْثُ شِئْتُمْ
رَغَدًا وَٱدْخُلُوا۟ ٱلْبَابَ سُجَّدًا وَقُولُوا۟ حِطَّةٌ نَّغْفِرْ لَكُمْ
خَطَٰيَٰكُمْ ۚ وَسَنَزِيدُ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٥٨﴾ فَبَدَّلَ ٱلَّذِينَ
ظَلَمُوا۟ قَوْلًا غَيْرَ ٱلَّذِى قِيلَ لَهُمْ فَأَنزَلْنَا عَلَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟
رِجْزًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ بِمَا كَانُوا۟ يَفْسُقُونَ ﴿٥٩﴾ ۞ وَإِذِ ٱسْتَسْقَىٰ
مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦ فَقُلْنَا ٱضْرِب بِّعَصَاكَ ٱلْحَجَرَ ۖ فَٱنفَجَرَتْ
مِنْهُ ٱثْنَتَا عَشْرَةَ عَيْنًا ۖ قَدْ عَلِمَ كُلُّ أُنَاسٍ مَّشْرَبَهُمْ ۖ كُلُوا۟
وَٱشْرَبُوا۟ مِن رِّزْقِ ٱللَّهِ وَلَا تَعْثَوْا۟ فِى ٱلْأَرْضِ مُفْسِدِينَ ﴿٦٠﴾
وَإِذْ قُلْتُمْ يَٰمُوسَىٰ لَن نَّصْبِرَ عَلَىٰ طَعَامٍ وَٰحِدٍ فَٱدْعُ لَنَا
رَبَّكَ يُخْرِجْ لَنَا مِمَّا تُنۢبِتُ ٱلْأَرْضُ مِنۢ بَقْلِهَا وَقِثَّآئِهَا
وَفُومِهَا وَعَدَسِهَا وَبَصَلِهَا ۖ قَالَ أَتَسْتَبْدِلُونَ ٱلَّذِى هُوَ
أَدْنَىٰ بِٱلَّذِى هُوَ خَيْرٌ ۚ ٱهْبِطُوا۟ مِصْرًا فَإِنَّ لَكُم مَّا سَأَلْتُمْ ۗ
وَضُرِبَتْ عَلَيْهِمُ ٱلذِّلَّةُ وَٱلْمَسْكَنَةُ وَبَآءُو بِغَضَبٍ مِّنَ
ٱللَّهِ ۗ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ كَانُوا۟ يَكْفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَيَقْتُلُونَ
ٱلنَّبِيِّـۧنَ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ ۗ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَوا۟ وَّكَانُوا۟ يَعْتَدُونَ ﴿٦١﴾

(58) Kuma ku tuna lokacin da Muka ce: “Ku shiga wannan alƙaryar ku ci daga (kayan marmarinta ta) inda kuka ga dama cikin yalwa, kuma ku shiga ƙofar garin a duƙe, kuma ku ce: “(Allah Ka) kankare mana laifuffukanmu”, za Mu gafarta muku laifuffukanku. Kuma za Mu ƙara wa masu kyautatawa

(59) Sai waɗanda suka yi zalunci suka canza maganar da aka faɗa musu, sai Muka saukar da wata azaba daga sama a kan waɗanda suka yi zalunci saboda abin da suke aikatawa na fasiƙanci

(60) Kuma ka tuna lokacin da Musa ya roƙa wa mutanensa ruwan sha, sai Muka ce: “Ka bugi dutse da sandarka”, sai idanuwan marmaron ruwa goma sha biyu suka ɓuɓɓugo daga cikinsa. Haƙiƙa kowaɗanne mutane sun san mashayarsu. (Muka ce): “Ku ci kuma ku sha daga arzikin Allah, kuma kada ku yaɗa ɓarna a bayan ƙasa

(61) Kuma ku tuna lokacin da kuka ce: “Ya Musa, ba za mu iya haƙuri a kan abinci iri ɗaya ba, don haka ka roƙa mana Ubangijinka Ya fitar mana (wani abincin) daga abin da ƙasa take tsirarwa, daga mabunƙusanta da gurjinta da alkamarta da wakenta da albasarta.” Sai ya ce, “Yanzu kwa nemi musanya ƙasƙantaccen abu da wanda yake shi ne mafifici? To ku sauka kowane gari, domin za ku samu abin da kuka roƙa (a cikinsa).” Don haka sai aka sanya musu ƙasƙanci da talauci, kuma suka koma da fushin Allah. Hakan ya faru gare su ne saboda sun kasance suna kafirce wa ayoyin Allah, kuma suna kashe annabawa ba tare da wani haƙƙi ba. Hakan ya faru saboda saɓon da suka yi da kuma ta’addancin da suka riƙa yi

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَٱلَّذِينَ هَادُواْ وَٱلنَّصَٰرَىٰ وَٱلصَّٰبِـِٔينَ مَنْ
ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَلَهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ
رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٦٢﴾ وَإِذْ أَخَذْنَا
مِيثَٰقَكُمْ وَرَفَعْنَا فَوْقَكُمُ ٱلطُّورَ خُذُواْ مَآ ءَاتَيْنَٰكُم
بِقُوَّةٍ وَٱذْكُرُواْ مَا فِيهِ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿٦٣﴾ ثُمَّ تَوَلَّيْتُم
مِّنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ ۖ فَلَوْلَا فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ لَكُنتُم مِّنَ
ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿٦٤﴾ وَلَقَدْ عَلِمْتُمُ ٱلَّذِينَ ٱعْتَدَوْاْ مِنكُمْ فِى ٱلسَّبْتِ
فَقُلْنَا لَهُمْ كُونُواْ قِرَدَةً خَٰسِـِٔينَ ﴿٦٥﴾ فَجَعَلْنَٰهَا نَكَٰلًا لِّمَا
بَيْنَ يَدَيْهَا وَمَا خَلْفَهَا وَمَوْعِظَةً لِّلْمُتَّقِينَ ﴿٦٦﴾ وَإِذْ قَالَ
مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦٓ إِنَّ ٱللَّهَ يَأْمُرُكُمْ أَن تَذْبَحُواْ بَقَرَةً ۖ قَالُوٓاْ
أَتَتَّخِذُنَا هُزُوًا ۖ قَالَ أَعُوذُ بِٱللَّهِ أَنْ أَكُونَ مِنَ ٱلْجَٰهِلِينَ
﴿٦٧﴾ قَالُواْ ٱدْعُ لَنَا رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا مَا هِىَ ۚ قَالَ إِنَّهُۥ يَقُولُ إِنَّهَا
بَقَرَةٌ لَّا فَارِضٌ وَلَا بِكْرٌ عَوَانٌۢ بَيْنَ ذَٰلِكَ ۖ فَٱفْعَلُواْ مَا
تُؤْمَرُونَ ﴿٦٨﴾ قَالُواْ ٱدْعُ لَنَا رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا مَا لَوْنُهَا ۚ قَالَ إِنَّهُۥ
يَقُولُ إِنَّهَا بَقَرَةٌ صَفْرَآءُ فَاقِعٌ لَّوْنُهَا تَسُرُّ ٱلنَّٰظِرِينَ ﴿٦٩﴾



(62) Lalle waɗanda suka yi imani da Yahudawa da Nasara da Sabi'awa(1), duk wanda ya yi imani da Allah da ranar Lahira kuma ya yi aiki na ƙwarai, to suna da ladansu a wurin Ubangijinsu, kuma babu tsoro a tare da su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba

(63) Kuma ku tuna lokacin da Muka ɗauki alƙawari mai ƙarfi daga gare ku, kuma Muka ɗaga dusten Ɗuri a kanku (Muka ce): "Ku karɓi abin da Muka ba ku da ƙarfi (Attaura), kuma ku tuna abin da yake cikinsa, don ku yi taƙawa."

(64) Sannan bayan haka sai kuka juya da baya, to ba domin falalar Allah da rahamarsa a gare ku ba, lalle da kun kasance daga cikin asararru

(65) Kuma haƙiƙa kun san waɗanda suka yi shisshigi daga cikinku game da ranar Assabar, sai Muka ce da su: "Ku zama birrai kuna ƙaskantattu."

(66) Sai Muka sanya ta (wannan ukubar) ta zama izina ga (al'ummomin) da suke zamanin faruwarta da kuma (garuruwan) da suke daura da su, kuma don ta zama wa'azi ga masu taƙawa

(67) Kuma ku tuna lokacin da Musa ya ce wa mutanensa: "Allah Yana umartar ku da ku yanka saniya", sai suka ce: "Yanzu ka riƙa yi mana izgili?" Sai ya ce: "Ina neman Allah Ya kiyaye ni da in zama cikin jahilai!"

(68) Sai suka ce: "Ka roƙa mana Ubangijinka Ya yi mana bayanin yaya take?" Sai ya ce: "Lalle Shi Yana cewa, lalle ita saniya ce, ba tsohuwa ba kuma ba budurwa ba, tana tsakatsakin haka." Don haka ku aikata abin da ake umartar ku

(69) Sai suka ce: "Ka roƙa mana Ubangijinka Ya bayyana mana mene ne launinta?" Sai ya ce, "Lalle Shi Yana cewa, lalle ita saniya ce mai launin fatsi-fatsi mai tsananin cizawa, tana faranta wa masu kallon ta rai."

(1) Waɗanda suka yi imani, su ne al'ummar Annabi Muhammadu ( ). Yahudawa, ana nufin mabiya Annabi Musa ( ) kafin a shafe addininsa, ko kafin su gurɓata shi. Nasara, ana nufin mabiya Annabi Isa ( ) kafin a shafe addininsa ko kafin su gurɓata shi. Sabi'awa, wasu ƙungiyoyi ne, daga cikinsu akwai masu aƙidar kaɗaita Allah da haramta duk wata alfasha da zalunci, duk da kasancewarsu ba bisa wani addini suke ba, to amma ba sa aikata shirka.

قَالُواْ ٱدۡعُ لَنَا رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا مَا هِيَ إِنَّ ٱلۡبَقَرَ تَشَٰبَهَ عَلَيۡنَا وَإِنَّآ
إِن شَآءَ ٱللَّهُ لَمُهۡتَدُونَ ٧٠ قَالَ إِنَّهُۥ يَقُولُ إِنَّهَا بَقَرَةٞ لَّا ذَلُولٞ
تُثِيرُ ٱلۡأَرۡضَ وَلَا تَسۡقِي ٱلۡحَرۡثَ مُسَلَّمَةٞ لَّا شِيَةَ فِيهَاۚ قَالُواْ
ٱلۡـَٰٔنَ جِئۡتَ بِٱلۡحَقِّۚ فَذَبَحُوهَا وَمَا كَادُواْ يَفۡعَلُونَ ٧١ وَإِذۡ
قَتَلۡتُمۡ نَفۡسٗا فَٱدَّٰرَٰٔتُمۡ فِيهَاۖ وَٱللَّهُ مُخۡرِجٞ مَّا كُنتُمۡ تَكۡتُمُونَ
٧٢ فَقُلۡنَا ٱضۡرِبُوهُ بِبَعۡضِهَاۚ كَذَٰلِكَ يُحۡيِ ٱللَّهُ ٱلۡمَوۡتَىٰ وَيُرِيكُمۡ
ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تَعۡقِلُونَ ٧٣ ثُمَّ قَسَتۡ قُلُوبُكُم مِّنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ
فَهِيَ كَٱلۡحِجَارَةِ أَوۡ أَشَدُّ قَسۡوَةٗۚ وَإِنَّ مِنَ ٱلۡحِجَارَةِ لَمَا يَتَفَجَّرُ
مِنۡهُ ٱلۡأَنۡهَٰرُۚ وَإِنَّ مِنۡهَا لَمَا يَشَّقَّقُ فَيَخۡرُجُ مِنۡهُ ٱلۡمَآءُۚ وَإِنَّ
مِنۡهَا لَمَا يَهۡبِطُ مِنۡ خَشۡيَةِ ٱللَّهِۗ وَمَا ٱللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ
٧٤ أَفَتَطۡمَعُونَ أَن يُؤۡمِنُواْ لَكُمۡ وَقَدۡ كَانَ فَرِيقٞ مِّنۡهُمۡ
يَسۡمَعُونَ كَلَٰمَ ٱللَّهِ ثُمَّ يُحَرِّفُونَهُۥ مِنۢ بَعۡدِ مَا عَقَلُوهُ وَهُمۡ
يَعۡلَمُونَ ٧٥ وَإِذَا لَقُواْ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا وَإِذَا
خَلَا بَعۡضُهُمۡ إِلَىٰ بَعۡضٖ قَالُوٓاْ أَتُحَدِّثُونَهُم بِمَا فَتَحَ ٱللَّهُ
عَلَيۡكُمۡ لِيُحَآجُّوكُم بِهِۦ عِندَ رَبِّكُمۡۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ٧٦

(70) Sai suka ce: “Ka roƙa mana Ubangijinka Ya bayyana mana yaya take, lalle shanu sun rikitar da mu, kuma lalle mu, insha Allahu masu shiryuwa ne.”

(71) Ya ce: “Lalle Shi Yana cewa, ita saniya ce wadda ba horarriya ba ce da take noma kasa, kuma ba ta shayar da shuka; lafiyayya ce, babu dabbare-dabbare a jikinta”. Sai suka ce: “Yanzu ne ka zo da gaskiya”. Sai suka yanka ta, kamar dai ba za su aikata ba

(72) Kuma ku tuna lokacin da kuka kashe wani mutum, kuma kuka riƙa tura wa juna (laifin kisan), Allah kuma Mai bayyanar da abin da kuka kasance kuna ɓoyewa ne

(73) Sai Muka ce: “Ku doke shi (mataccen) da wani sashinta (saniyar).”[1] Kamar haka ne Allah Yake raya matattu, Yake kuma nuna muku ayoyinsa don ku hankalta

(74) Sannan sai zukatanku suka ƙeƙashe bayan haka, suka zama kamar dutse ko ma fiye da dutse ƙeƙashewa. Kuma lalle daga cikin duwatsu akwai waɗanda ƙoramu suke ɓuɓɓugowa daga cikinsu; akwai kuma waɗanda suke tsattsagewa ruwa ya fito daga cikinsu; akwai kuma waɗanda suke faɗowa saboda tsoron Allah. Allah ba marafkani ne ba game da abin da kuke aikatawa

(75) Yanzu (ku muminai) kwa sa ran su yi imani saboda ku, alhalin wata ƙungiya daga cikinsu suna sauraron maganar Allah sannan su jirkita ta bayan sun fahimce ta alhalin kuwa suna sane?

(76) Kuma idan suka haɗu da waɗanda suka yi imani sai su ce: “Mun yi imani”, amma kuma idan sashinsu ya keɓance da sashi sai su ce: “Yanzu kwa riƙa faɗa musu abin da Allah Ya yi muku buɗi da shi don su kafa muku hujja da shi a wurin Ubangijinku? Shin ba za ku hankalta ba?”

(1) Sai Allah ya sake raya shi, ya tashi ya faɗa musu sunan wanda ya kashe shi.

أَوَلَا يَعْلَمُونَ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعْلِنُونَ ﴿٧٧﴾
وَمِنْهُمْ أُمِّيُّونَ لَا يَعْلَمُونَ ٱلْكِتَٰبَ إِلَّآ أَمَانِيَّ وَإِنْ هُمْ
إِلَّا يَظُنُّونَ ﴿٧٨﴾ فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ يَكْتُبُونَ ٱلْكِتَٰبَ بِأَيْدِيهِمْ
ثُمَّ يَقُولُونَ هَٰذَا مِنْ عِندِ ٱللَّهِ لِيَشْتَرُوا۟ بِهِۦ ثَمَنًا قَلِيلًا ۖ
فَوَيْلٌ لَّهُم مِّمَّا كَتَبَتْ أَيْدِيهِمْ وَوَيْلٌ لَّهُمْ مِّمَّا يَكْسِبُونَ
﴿٧٩﴾ وَقَالُوا۟ لَن تَمَسَّنَا ٱلنَّارُ إِلَّآ أَيَّامًا مَّعْدُودَةً ۚ قُلْ
أَتَّخَذْتُمْ عِندَ ٱللَّهِ عَهْدًا فَلَن يُخْلِفَ ٱللَّهُ عَهْدَهُۥٓ ۖ أَمْ
تَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿٨٠﴾ بَلَىٰ ۚ مَن كَسَبَ سَيِّئَةً
وَأَحَاطَتْ بِهِۦ خَطِيٓـَٔتُهُۥ فَأُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ ۖ هُمْ
فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿٨١﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ ۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿٨٢﴾ وَإِذْ أَخَذْنَا
مِيثَٰقَ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ لَا تَعْبُدُونَ إِلَّا ٱللَّهَ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ
إِحْسَانًا وَذِى ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينِ وَقُولُوا۟
لِلنَّاسِ حُسْنًا وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ ثُمَّ
تَوَلَّيْتُمْ إِلَّا قَلِيلًا مِّنكُمْ وَأَنتُم مُّعْرِضُونَ ﴿٨٣﴾

(77) Shin ko ba su san Allah Yana sane da abin da suke ɓoyewa da abin da suke bayyanawa ba?
(78) Kuma daga cikinsu akwai jahilai waɗanda ba su san Littafi ba sai burace-burace, kuma zato kawai suke yi
(79) To tsananin azaba ya tabbata ga waɗanda suke rubuta littafi da hannayensu sannan su ce: "Wannan daga Allah yake", don su musanya shi da wani ɗan kuɗi kaɗan. To tsananin azaba ya tabbata a gare su saboda abin da hannayensu suka rubuta, kuma tsananin azaba ya tabbata a gare su saboda abin da suka kasance suna tsuwurwuta
(80) Kuma suka ce: "Wuta ba za ta shafe mu ba sai cikin wasu 'yan kwanaki ƙididdigaggu." Ka ce: "Shin kun yi wani alƙawari ne da Allah, don haka Allah ba zai saɓa alƙawarinsa ba? Ko kuma kuna faɗar abin da ba ku da ilimi ne kuna jingina wa Allah?"
(81) E! Wanda duk ya aikata mummunan aiki kuma laifuffukansa suka kewaye shi, to waɗannan su ne 'yan wuta, su masu dawwama ne a cikinta
(82) Waɗanda kuma suka yi imani kuma suka yi ayyuka na ƙwarai, to waɗannan 'yan Aljanna ne, kuma su masu dawwama ne a cikinta
(83) Kuma ka tuna lokacin da Muka ɗauki alƙwari daga Banu Isra'ila cewa, ba za ku bauta wa kowa ba sai Allah, kuma za ku kyautata wa iyaye da makusanta da marayu da miskinai, kuma ku rika yi wa mutane kyakkyawar magana, kuma ku tsai da salla, kuma ku ba da zakka, sannan sai kuka ba da baya sai 'yan kaɗan daga cikinku, alhalin kuna masu bijirewa

وَإِذْ أَخَذْنَا مِيثَٰقَكُمْ لَا تَسْفِكُونَ دِمَآءَكُمْ وَلَا تُخْرِجُونَ
أَنفُسَكُم مِّن دِيَٰرِكُمْ ثُمَّ أَقْرَرْتُمْ وَأَنتُمْ تَشْهَدُونَ ﴿٨٤﴾
ثُمَّ أَنتُمْ هَٰٓؤُلَآءِ تَقْتُلُونَ أَنفُسَكُمْ وَتُخْرِجُونَ فَرِيقًا
مِّنكُم مِّن دِيَٰرِهِمْ تَظَٰهَرُونَ عَلَيْهِم بِٱلْإِثْمِ وَٱلْعُدْوَٰنِ
وَإِن يَأْتُوكُمْ أُسَٰرَىٰ تُفَٰدُوهُمْ وَهُوَ مُحَرَّمٌ عَلَيْكُمْ
إِخْرَاجُهُمْ ۚ أَفَتُؤْمِنُونَ بِبَعْضِ ٱلْكِتَٰبِ وَتَكْفُرُونَ بِبَعْضٍ ۚ
فَمَا جَزَآءُ مَن يَفْعَلُ ذَٰلِكَ مِنكُمْ إِلَّا خِزْىٌ فِى ٱلْحَيَوٰةِ
ٱلدُّنْيَا ۖ وَيَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يُرَدُّونَ إِلَىٰٓ أَشَدِّ ٱلْعَذَابِ ۗ وَمَا ٱللَّهُ
بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿٨٥﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱشْتَرَوُا۟ ٱلْحَيَوٰةَ
ٱلدُّنْيَا بِٱلْءَاخِرَةِ ۖ فَلَا يُخَفَّفُ عَنْهُمُ ٱلْعَذَابُ وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ
﴿٨٦﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ وَقَفَّيْنَا مِنۢ بَعْدِهِۦ
بِٱلرُّسُلِ ۖ وَءَاتَيْنَا عِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ ٱلْبَيِّنَٰتِ وَأَيَّدْنَٰهُ بِرُوحِ
ٱلْقُدُسِ ۗ أَفَكُلَّمَا جَآءَكُمْ رَسُولٌۢ بِمَا لَا تَهْوَىٰٓ أَنفُسُكُمُ
ٱسْتَكْبَرْتُمْ فَفَرِيقًا كَذَّبْتُمْ وَفَرِيقًا تَقْتُلُونَ ﴿٨٧﴾ وَقَالُوا۟ قُلُوبُنَا
غُلْفٌۢ ۚ بَل لَّعَنَهُمُ ٱللَّهُ بِكُفْرِهِمْ فَقَلِيلًا مَّا يُؤْمِنُونَ ﴿٨٨﴾

(84) Kuma ku tuna lokacin da Muka ɗauki alƙawari da ku cewa, ba za ku zubar da jinanenku ba, kuma ba za ku fitar da junanku daga gidajenku ba, sannan kuka tabbatar da hakan, alhalin kuna masu shaida

(85) Sannan sai ga ku, ku ɗin nan kuna kashe junanku, kuma kuna fitar da wata ƙungiya daga cikinku daga gidajensu, kuma kuna taimaka wa juna wajen cutar da su ta hanyar laifi da zalunci. Idan kuma sun zo muku suna kamammun yaƙi sai ku fanshe su, alhali fitar da su haramun ne a gare ku.

Yanzu kwa riƙa yin imani da sashen Littafi kuma ku riƙa kafircewa da wani sashen? To ba komai ne sakamakon wanda yake aikata haka daga cikinku ba face wani wulaƙanci a rayuwar duniya, kuma ranar alƙiyama a mayar da su zuwa ga mafi tsananin azaba, kuma Allah ba rafkananne ba ne game da abin da kuke aikatawa

(86) Waɗannan su ne waɗanda suka musanya rayuwar duniya da ta lahira, kuma ba za a sassauta musu azaba ba, kuma ba za a taimaka musu ba

(87) Kuma haƙiƙa Mun ba wa Musa Littafi, kuma Muka biyo bayansa da manzanni, kuma Mun bai wa Isa ɗan Maryam hujjoji bayyananu, kuma Mun ƙarfafe shi da Ruhi mai tsarki. Ashe yanzu duk sa'adda wani manzo ya zo muku da abin da zukatanku ba sa so, sai ku yi girman kai, don haka sai ku ƙaryata wasu, kuma ku kashe wasu?

(88) Suka ce kuma: "Zukatanmu rufaffu ne." A'a ba haka ba ne, Allah dai Ya la'ane su ne saboda kafircinsu, don haka kaɗan ne waɗanda suke yin imani

وَلَمَّا جَآءَهُمْ كِتَٰبٌ مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ مُصَدِّقٌ لِّمَا مَعَهُمْ
وَكَانُوا۟ مِن قَبْلُ يَسْتَفْتِحُونَ عَلَى ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ فَلَمَّا
جَآءَهُم مَّا عَرَفُوا۟ كَفَرُوا۟ بِهِۦ ۚ فَلَعْنَةُ ٱللَّهِ عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ
﴿٨٩﴾ بِئْسَمَا ٱشْتَرَوْا۟ بِهِۦٓ أَنفُسَهُمْ أَن يَكْفُرُوا۟ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ
بَغْيًا أَن يُنَزِّلَ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ ۖ
فَبَآءُو بِغَضَبٍ عَلَىٰ غَضَبٍ ۚ وَلِلْكَٰفِرِينَ عَذَابٌ مُّهِينٌ
﴿٩٠﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ ءَامِنُوا۟ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ قَالُوا۟ نُؤْمِنُ بِمَآ أُنزِلَ
عَلَيْنَا وَيَكْفُرُونَ بِمَا وَرَآءَهُۥ وَهُوَ ٱلْحَقُّ مُصَدِّقًا لِّمَا
مَعَهُمْ ۗ قُلْ فَلِمَ تَقْتُلُونَ أَنۢبِيَآءَ ٱللَّهِ مِن قَبْلُ إِن كُنتُم
مُّؤْمِنِينَ ﴿٩١﴾ * وَلَقَدْ جَآءَكُم مُّوسَىٰ بِٱلْبَيِّنَٰتِ ثُمَّ
ٱتَّخَذْتُمُ ٱلْعِجْلَ مِنۢ بَعْدِهِۦ وَأَنتُمْ ظَٰلِمُونَ ﴿٩٢﴾ وَإِذْ
أَخَذْنَا مِيثَٰقَكُمْ وَرَفَعْنَا فَوْقَكُمُ ٱلطُّورَ خُذُوا۟
مَآ ءَاتَيْنَٰكُم بِقُوَّةٍ وَٱسْمَعُوا۟ ۖ قَالُوا۟ سَمِعْنَا وَعَصَيْنَا
وَأُشْرِبُوا۟ فِى قُلُوبِهِمُ ٱلْعِجْلَ بِكُفْرِهِمْ ۚ قُلْ بِئْسَمَا
يَأْمُرُكُم بِهِۦٓ إِيمَٰنُكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٩٣﴾

(89) Yayin da kuma wani littafi ya zo musu daga Allah, yana mai gaskata abin da yake tare da su, alhali kuma a da sun kasance suna addu'ar neman nasara a kan waɗanda suka kafirta (mushrikai). To yayin da abin da suka sani ya zo musu sai suka kafirce masa(1). Don haka la'anar Allah ta tabbata a kan kafirai

(90) Tir da wannan abu da suka sayar da kawunansu da shi, wato suka kafirce wa abin da Allah Ya saukar, don hassadar cewa, (don me) Allah zai saukar da falalarsa ga wanda Ya ga dama daga bayinsa, sai suka wayi gari da fushin Allah a kan wani fushin. Kuma azaba ta wulaƙanci ta tabbata ga kafirai

(91) Idan aka ce da su: "Ku yi imani da abin da Allah Ya saukar", sai su ce: "Mu muna yin imani ne da abin da aka saukar mana". Kuma suna kafircewa da duk wani abu da ba shi ba, alhalin shi gaskiya ne, kuma mai gaskata abin da ke tare da su ne. To ka ce: "Me ya sa a da kuke kashe annabawan Allah idan kun kasance muminai?"

(92) Haƙiƙa Musa ya zo muku da hujjoji bayyanannu, sannan kuka bauta wa ɗan maraƙi bayansa alhalin kuna azzalumai

(93) Kuma ku tuna lokacin da Muka ɗauki alƙawari da ku, Muka kuma ɗaga dutsen Duri a kanku, Muka ce: "Ku riƙi abin da muka ba ku da ƙarfi, kuma ku saurara". Sai suka ce: "Mun ji kuma mun saɓa". Kuma aka sanya musu tsananin son bautar ɗan maraƙi a zukatansu saboda kafircinsu. Ka ce: "Tir da abin da imaninku yake umartar ku da shi, idan har kun kasance muminai."

(1) Kafin aiko Annabi Muhammadu ( ), idan faɗa ya ɓarke tsaknin Yahudu da Larabawa, Yahudu sukan ce, za a aiko wani annabi, idan ya bayyana za mu bi shi, mu haɗa ƙarfi da shi mu yaƙe ku. Yayin da Annabi ( ) ya bayyana ba a cikinsu ba sai suka kafirce masa.

قُلْ إِن كَانَتْ لَكُمُ ٱلدَّارُ ٱلْآخِرَةُ عِندَ ٱللَّهِ خَالِصَةً مِّن
دُونِ ٱلنَّاسِ فَتَمَنَّوُا۟ ٱلْمَوْتَ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٩٤﴾ وَلَن
يَتَمَنَّوْهُ أَبَدًۢا بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِٱلظَّٰلِمِينَ
﴿٩٥﴾ وَلَتَجِدَنَّهُمْ أَحْرَصَ ٱلنَّاسِ عَلَىٰ حَيَوٰةٍ وَمِنَ ٱلَّذِينَ أَشْرَكُوا۟ ۛ
يَوَدُّ أَحَدُهُمْ لَوْ يُعَمَّرُ أَلْفَ سَنَةٍ وَمَا هُوَ بِمُزَحْزِحِهِۦ مِنَ
ٱلْعَذَابِ أَن يُعَمَّرَ ۗ وَٱللَّهُ بَصِيرٌۢ بِمَا يَعْمَلُونَ ﴿٩٦﴾ قُلْ مَن
كَانَ عَدُوًّا لِّجِبْرِيلَ فَإِنَّهُۥ نَزَّلَهُۥ عَلَىٰ قَلْبِكَ بِإِذْنِ
ٱللَّهِ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ وَهُدًى وَبُشْرَىٰ لِلْمُؤْمِنِينَ
﴿٩٧﴾ مَن كَانَ عَدُوًّا لِّلَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَرُسُلِهِۦ وَجِبْرِيلَ
وَمِيكَىٰلَ فَإِنَّ ٱللَّهَ عَدُوٌّ لِّلْكَٰفِرِينَ ﴿٩٨﴾ وَلَقَدْ أَنزَلْنَآ
إِلَيْكَ ءَايَٰتٍۭ بَيِّنَٰتٍ ۖ وَمَا يَكْفُرُ بِهَآ إِلَّا ٱلْفَٰسِقُونَ ﴿٩٩﴾
أَوَكُلَّمَا عَٰهَدُوا۟ عَهْدًا نَّبَذَهُۥ فَرِيقٌ مِّنْهُم ۚ بَلْ أَكْثَرُهُمْ
لَا يُؤْمِنُونَ ﴿١٠٠﴾ وَلَمَّا جَآءَهُمْ رَسُولٌ مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ مُصَدِّقٌ
لِّمَا مَعَهُمْ نَبَذَ فَرِيقٌ مِّنَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ
كِتَٰبَ ٱللَّهِ وَرَآءَ ظُهُورِهِمْ كَأَنَّهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٠١﴾

(94) Ka ce: “Idan gidan lahira ya kasance keɓantacce a gare ku a wurin Allah ku kaɗai ban da sauran mutane, to ku yi burin mutuwa idan har ku masu gaskiya ne.”

(95) Ba za su taɓa burin mutuwa ba har abada, saboda abin da hannayensu suka aikata. Kuma Allah Masani ne ga azzalumai

(96) Kuma lalle za ka same su sun fi kowa kwaɗayin tsawon rai, fiye ma da waɗanda suka yi shirka. Kowane ɗayansu yana burin ina ma za a raya shi shekara dubu. Hakan kuma ba zai nesanta shi daga azaba ba don an yi masa tsawon rai. Kuma Allah Mai ganin abin da suka kasance suna aikatawa ne

(97) Ka ce: “Duk wanda ya kasance maƙiyi ne ga (Mala’ika) Jibrilu[1], to lalle shi ne ya saukar da shi (Alƙur’ani) a kan zuciyarka da izinin Allah yana mai gaskata abin da ya gabace shi (na littattafai), kuma shiriya ne da bushara ga muminai.”

(98) Duk wanda ya kasance maƙiyi ne ga Allah da mala’ikunsa da manzanninsa da Jibrilu da Mika’ilu, to lalle Allah maƙiyin kafirai ne

(99) Kuma haƙiƙa Mun saukar maka da ayoyi bayyanannu, babu kuma mai kafirce musu sai fasiƙai

(100) Yanzu ashe duk sa’adda suka ƙulla wani alƙawari sai wani ɓangare daga cikinsu ya yi watsi da shi?! Bari! Yawancinsu ba sa yin imani

(101) Yayin da wani manzo daga Allah ya zo musu yana mai gaskata abin da yake tare da su (na Littafin Attaura), sai wani ɓangare daga cikinsu suka jefar da littafin Allah a bayansu kamar ba su san komai ba

(1) Yahudawa sun faɗa wa Annabi cewa, Mala'ika Jibrilu maƙiyinsu ne, wai domin shi ne yake saukowa da yaƙi da kashe-kashe da azaba.

وَٱتَّبَعُواْ مَا تَتْلُواْ ٱلشَّيَٰطِينُ عَلَىٰ مُلْكِ سُلَيْمَٰنَ ۖ وَمَا كَفَرَ
سُلَيْمَٰنُ وَلَٰكِنَّ ٱلشَّيَٰطِينَ كَفَرُواْ يُعَلِّمُونَ ٱلنَّاسَ
ٱلسِّحْرَ وَمَآ أُنزِلَ عَلَى ٱلْمَلَكَيْنِ بِبَابِلَ هَٰرُوتَ وَمَٰرُوتَ ۚ
وَمَا يُعَلِّمَانِ مِنْ أَحَدٍ حَتَّىٰ يَقُولَآ إِنَّمَا نَحْنُ فِتْنَةٌ فَلَا
تَكْفُرْ ۖ فَيَتَعَلَّمُونَ مِنْهُمَا مَا يُفَرِّقُونَ بِهِۦ بَيْنَ ٱلْمَرْءِ
وَزَوْجِهِۦ ۚ وَمَا هُم بِضَآرِّينَ بِهِۦ مِنْ أَحَدٍ إِلَّا بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۚ
وَيَتَعَلَّمُونَ مَا يَضُرُّهُمْ وَلَا يَنفَعُهُمْ ۚ وَلَقَدْ عَلِمُواْ لَمَنِ
ٱشْتَرَىٰهُ مَا لَهُۥ فِى ٱلْءَاخِرَةِ مِنْ خَلَٰقٍ ۚ وَلَبِئْسَ مَا شَرَوْاْ بِهِۦٓ
أَنفُسَهُمْ ۚ لَوْ كَانُواْ يَعْلَمُونَ ﴿١٠٢﴾ وَلَوْ أَنَّهُمْ ءَامَنُواْ وَٱتَّقَوْاْ
لَمَثُوبَةٌ مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ خَيْرٌ ۚ لَّوْ كَانُواْ يَعْلَمُونَ ﴿١٠٣﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقُولُواْ رَٰعِنَا وَقُولُواْ ٱنظُرْنَا
وَٱسْمَعُواْ ۗ وَلِلْكَٰفِرِينَ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿١٠٤﴾ مَّا يَوَدُّ
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ وَلَا ٱلْمُشْرِكِينَ
أَن يُنَزَّلَ عَلَيْكُم مِّنْ خَيْرٍ مِّن رَّبِّكُمْ ۚ وَٱللَّهُ يَخْتَصُّ
بِرَحْمَتِهِۦ مَن يَشَآءُ ۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلْفَضْلِ ٱلْعَظِيمِ ﴿١٠٥﴾

(102) Sai suka bi abin da shedanu suke karantawa a (zamanin) mulkin Sulaimanu; kuma Sulaimanu bai kafirta ba, sai dai shedanun su ne suka kafirta; suna koya wa mutane tsafi da abin da aka saukar wa mala'iku biyu, Haruta da Maruta, a garin Babila. Kuma ba sa koya wa wani (tsafin) har sai sun fada masa cewa: "Mu fa jarraba ce, don haka kada ka kafirta". Sai (mutane) suka rika koyo daga wajensu su biyu abin da suke raba tsakanin miji da matarsa da shi. Kuma ba za su iya cutar da wani da shi ba sai da izinin Allah. Sai su koyi abin da zai cutar da su kuma ba zai amfane su ba. Kuma hakika sun san cewa, tabbas duk wanda ya zabi (sihiri) ba shi da wani rabo a lahira. Kuma lalle tir da abin da suka sayar da kawunansu da shi, da a ce sun san (hakikanin makomarsu)

(103) Da a ce su sun yi imani kuma sun yi takawa, hakika da sakamakon (da za su samu) daga Allah shi ne mafi alheri, da a ce sun sani

(104) Ya ku wadanda suka yi imani kada ku ce, ra'ina, (watau kula da mu), sai dai ku ce, dakata mana(1), kuma ku saurara. Kafirai kuma suna da wata azaba mai radadi

(105) Wadanda suka kafirta daga ma'abota littafi da mushrikai ba sa kaunar a saukar muku da wani alheri daga Ubangijinku, sai dai Allah kuwa Yana kebance wanda Ya ga dama da rahamarsa, Allah kuma Mai babbar falala ne

(1) Sahabban Annabi ( ) sun kasance idan yana biya musu karatu sukan nemi ya dan dakata musu kadan domin su fahimta sosai, to sai sukan yi amfani da kalmar 'ra'ina'. A harshen Yahudawa kuma kalmar tana kusa da wata kalma da take da ma'anar 'dakiki', to sai su ma suka rika fakewa da wannan kalmar suna zagin Annabi ( ). Sai Allah ya hana sahabbai amfani da kalmar, a maimakonta ya ce su yi amfani da kalmar 'unzurna' wadda take nufin 'dakata mana'.

مَا نَنسَخْ مِنْ ءَايَةٍ أَوْ نُنسِهَا نَأْتِ بِخَيْرٍ مِّنْهَآ أَوْ مِثْلِهَآ ۗ
أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿١٠٦﴾ أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ
ٱللَّهَ لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ
ٱللَّهِ مِن وَلِىٍّ وَلَا نَصِيرٍ ﴿١٠٧﴾ أَمْ تُرِيدُونَ أَن تَسْـَٔلُوا۟ رَسُولَكُمْ
كَمَا سُئِلَ مُوسَىٰ مِن قَبْلُ ۗ وَمَن يَتَبَدَّلِ ٱلْكُفْرَ بِٱلْإِيمَٰنِ
فَقَدْ ضَلَّ سَوَآءَ ٱلسَّبِيلِ ﴿١٠٨﴾ وَدَّ كَثِيرٌ مِّنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ
لَوْ يَرُدُّونَكُم مِّنۢ بَعْدِ إِيمَٰنِكُمْ كُفَّارًا حَسَدًا
مِّنْ عِندِ أَنفُسِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلْحَقُّ ۖ فَٱعْفُوا۟
وَٱصْفَحُوا۟ حَتَّىٰ يَأْتِىَ ٱللَّهُ بِأَمْرِهِۦٓ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ
قَدِيرٌ ﴿١٠٩﴾ وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ ۚ وَمَا تُقَدِّمُوا۟
لِأَنفُسِكُم مِّنْ خَيْرٍ تَجِدُوهُ عِندَ ٱللَّهِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِمَا تَعْمَلُونَ
بَصِيرٌ ﴿١١٠﴾ وَقَالُوا۟ لَن يَدْخُلَ ٱلْجَنَّةَ إِلَّا مَن كَانَ هُودًا
أَوْ نَصَٰرَىٰ ۗ تِلْكَ أَمَانِيُّهُمْ ۗ قُلْ هَاتُوا۟ بُرْهَٰنَكُمْ إِن كُنتُمْ
صَٰدِقِينَ ﴿١١١﴾ بَلَىٰ مَنْ أَسْلَمَ وَجْهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحْسِنٌ فَلَهُۥٓ
أَجْرُهُۥ عِندَ رَبِّهِۦ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿١١٢﴾

(106) Babu wata aya da za Mu shafe ko Mu mantar da kai ita, sai Mun kawo wadda ta fi ta alheri ko kwatankwacinta. Ashe ba ka san cewa, lalle Allah Mai iko ne a kan komai ba?
(107) Kuma ba ka sani ba cewa, lalle mulkin sammai da ƙasa na Allah ne, kuma ba ku da wani majiɓinci ko wani mai taimako ba Allah ba?
(108) Ko kuma kuna nufin za ku tambayi Manzonku kamar yadda aka yi wa Musa tambaya a da? Kuma duk wanda ya canza imani da kafirci to haƙiƙa ya ɓace wa hanya tsakatsakiya

(109) Da yawa daga cikin ma'abota littafi sun yi burin ina ma a ce su mayar da ku kafirai bayan imaninku, saboda hassada daga zukatansu, bayan kuma gaskiya ta bayyana a gare su. Don haka ku yi afuwa ku kawar da kai har sai Allah Ya zo da al'amarinsa. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai
(110) Kuma ku tsayar da salla ku kuma ba da zakka; kuma duk abin da kuka aikata na alheri domin kawunanku za ku same shi a wajen Allah. Lalle Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne
(111) Kuma (Yahudawa da Nasara) suka ce: "Babu mai shiga Aljanna sai wanda ya kasance Bayahude ko Banasare". Waɗannan burace-buracensu ne. Ka ce: "Ku kawo hujjarku idan kun kasance masu gaskiya"
(112) E! Wanda ya miƙa fuskarsa ga Allah alhali yana mai kyautata aikinsa, to yana da ladansa a wajen Ubangijinsa, kuma babu tsoro a tare da su kuma ba za su yi baƙin ciki ba

وَقَالَتِ ٱلْيَهُودُ لَيْسَتِ ٱلنَّصَٰرَىٰ عَلَىٰ شَىْءٍ وَقَالَتِ ٱلنَّصَٰرَىٰ
لَيْسَتِ ٱلْيَهُودُ عَلَىٰ شَىْءٍ وَهُمْ يَتْلُونَ ٱلْكِتَٰبَ ۗ كَذَٰلِكَ
قَالَ ٱلَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ مِثْلَ قَوْلِهِمْ ۚ فَٱللَّهُ يَحْكُمُ بَيْنَهُمْ
يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُوا۟ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿١١٣﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن
مَّنَعَ مَسَٰجِدَ ٱللَّهِ أَن يُذْكَرَ فِيهَا ٱسْمُهُۥ وَسَعَىٰ فِى خَرَابِهَآ ۚ
أُو۟لَٰٓئِكَ مَا كَانَ لَهُمْ أَن يَدْخُلُوهَآ إِلَّا خَآئِفِينَ ۚ لَهُمْ فِى
ٱلدُّنْيَا خِزْىٌ وَلَهُمْ فِى ٱلْءَاخِرَةِ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿١١٤﴾ وَلِلَّهِ ٱلْمَشْرِقُ
وَٱلْمَغْرِبُ ۚ فَأَيْنَمَا تُوَلُّوا۟ فَثَمَّ وَجْهُ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ﴿١١٥﴾
وَقَالُوا۟ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدًا ۗ سُبْحَٰنَهُۥ ۖ بَل لَّهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ ۖ كُلٌّ لَّهُۥ قَٰنِتُونَ ﴿١١٦﴾ بَدِيعُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ
وَإِذَا قَضَىٰٓ أَمْرًا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿١١٧﴾ وَقَالَ
ٱلَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ لَوْلَا يُكَلِّمُنَا ٱللَّهُ أَوْ تَأْتِينَآ ءَايَةٌ ۗ
كَذَٰلِكَ قَالَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِم مِّثْلَ قَوْلِهِمْ ۘ تَشَٰبَهَتْ
قُلُوبُهُمْ ۗ قَدْ بَيَّنَّا ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يُوقِنُونَ ﴿١١٨﴾ إِنَّآ أَرْسَلْنَٰكَ
بِٱلْحَقِّ بَشِيرًا وَنَذِيرًا ۖ وَلَا تُسْـَٔلُ عَنْ أَصْحَٰبِ ٱلْجَحِيمِ ﴿١١٩﴾

(113) Yahudawa suka ce: “Nasara ba a kan komai suke ba”, su ma Nasara suka ce: “Yahudawa ba a kan komai suke ba”, alhalin dukkansu suna karanta Littafi. Kamar haka ne waɗanda ba su da ilimi suka yi irin maganarsu. Kuma Allah zai yi hukunci a tsakaninsu ranar Alƙiyama a kan abin da suka kasance suna saɓani a cikinsa

(114) Wane ne mafi zalunci kamar wanda ya hana masallatan Allah a riƙa ambaton sunansa a cikinsu, ya yi ta ƙoƙari wajen rushe su? Waɗannan bai kamata su shige su ba sai a cikin halin tsoro. Za su gamu da wulaƙanci a duniya a lahira kuma suna da wata azaba mai girma

(115) Gabas da yamma kuma na Allah ne. Duk inda aka fuskantar da ku to can ma alƙiblar Allah ce. Lalle Allah Mai yalwar falala ne, kuma Mai yawan sani

(116) Kuma suka ce: “Allah Yana da ɗa”. Tsarki ya tabbata a gare Shi. Bari (wannan magana)! Duk abin da yake cikin sammai da ƙasa nasa ne, kuma dukkansu masu biyayya ne a gare Shi

(117) Shi ne Maƙirƙirin halittar sammai da ƙasa; kuma idan zai zartar da wani al’amari sai kawai Ya ce da shi: “Kasance”, sai ya kasance

(118) Waɗanda ba su da ilimi kuma suka ce, “Me zai hana Allah Ya yi magana da mu ko kuma wata aya ta zo mana?” Kamar haka ne waɗanda suka gabace su suka faɗi irin wannan maganar tasu. Zukatansu sun yi kama da juna. Haƙiƙa mun yi bayanin ayoyi ga mutane masu sakankancewa

(119) Lalle Mu Mun aiko ka da gaskiya, kana mai albishir kuma kana mai gargaɗi, ba kuma za a tambaye ka ba game da ‘yan wutar Jahima

وَلَن تَرۡضَىٰ عَنكَ ٱلۡيَهُودُ وَلَا ٱلنَّصَٰرَىٰ حَتَّىٰ تَتَّبِعَ مِلَّتَهُمۡۗ قُلۡ
إِنَّ هُدَى ٱللَّهِ هُوَ ٱلۡهُدَىٰۗ وَلَئِنِ ٱتَّبَعۡتَ أَهۡوَآءَهُم بَعۡدَ ٱلَّذِي
جَآءَكَ مِنَ ٱلۡعِلۡمِ مَا لَكَ مِنَ ٱللَّهِ مِن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٍ ١٢٠ ٱلَّذِينَ
ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ يَتۡلُونَهُۥ حَقَّ تِلَاوَتِهِۦٓ أُوْلَٰٓئِكَ يُؤۡمِنُونَ بِهِۦۗ وَمَن
يَكۡفُرۡ بِهِۦ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ١٢١ يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَتِيَ
ٱلَّتِيٓ أَنۡعَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ وَأَنِّي فَضَّلۡتُكُمۡ عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٢٢ وَٱتَّقُواْ يَوۡمٗا
لَّا تَجۡزِي نَفۡسٌ عَن نَّفۡسٖ شَيۡـٔٗا وَلَا يُقۡبَلُ مِنۡهَا عَدۡلٞ وَلَا تَنفَعُهَا
شَفَٰعَةٞ وَلَا هُمۡ يُنصَرُونَ ١٢٣ ۞ وَإِذِ ٱبۡتَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِـۧمَ رَبُّهُۥ بِكَلِمَٰتٖ
فَأَتَمَّهُنَّۖ قَالَ إِنِّي جَاعِلُكَ لِلنَّاسِ إِمَامٗاۖ قَالَ وَمِن ذُرِّيَّتِيۖ قَالَ
لَا يَنَالُ عَهۡدِي ٱلظَّٰلِمِينَ ١٢٤ وَإِذۡ جَعَلۡنَا ٱلۡبَيۡتَ مَثَابَةٗ لِّلنَّاسِ
وَأَمۡنٗا وَٱتَّخِذُواْ مِن مَّقَامِ إِبۡرَٰهِـۧمَ مُصَلّٗىۖ وَعَهِدۡنَآ إِلَىٰٓ إِبۡرَٰهِـۧمَ
وَإِسۡمَٰعِيلَ أَن طَهِّرَا بَيۡتِيَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلۡعَٰكِفِينَ وَٱلرُّكَّعِ ٱلسُّجُودِ
١٢٥ وَإِذۡ قَالَ إِبۡرَٰهِـۧمُ رَبِّ ٱجۡعَلۡ هَٰذَا بَلَدًا ءَامِنٗا وَٱرۡزُقۡ أَهۡلَهُۥ
مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ مَنۡ ءَامَنَ مِنۡهُم بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۖ قَالَ وَمَن كَفَرَ
فَأُمَتِّعُهُۥ قَلِيلٗا ثُمَّ أَضۡطَرُّهُۥٓ إِلَىٰ عَذَابِ ٱلنَّارِۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ١٢٦

(120) Yahudawa da Nasara ba za su taɓa yarda da kai ba har sai ka bi addininsu. Ka ce: "Shiriyar Allah lalle ita ce shiriya". Idan har ka bi son zuciyarsu bayan abin da ya zo maka na gaskiya, to ba ka da wani majiɓinci ko mai taimakonka wajen Allah

(121) Waɗanda Muka saukar musu da littafi suna karanta shi yadda ya cancanta a karanta shi, waɗannan su ne suke yin imani da shi. Kuma waɗanda suka kafirce masa to waɗannan su ne hasararru

(122) Ya ku Banu Isra'ila, ku tuna ni'imar da Na yi muku, kuma lalle Ni Na fifita ku a kan sauran mutanen duniya (na zamaninku)

(123) Kuma ku kiyayi wani yini da wani rai ba zai isar wa da wani rai komai ba, kuma ba za a karɓi wata fansa daga gare shi ba, kuma ceto ba zai amfane shi ba, kuma su ba za a taimaka musu ba (124) Kuma ka tuna lokacin da Ubangijin Ibrahimu Ya jarrabe shi da wasu kalmomi, sai ya cika su, sai Ya ce: "Ni zan naɗa ka shugaba ga mutane". Sai (Ibrahimu) ya ce: "Har da kuma zurriyata"; Sai (Allah) Ya ce: "Alƙawarina ba zai shafi azzalumai ba."

(125) Kuma ka tuna lokacin da Muka sanya wannan Daki ya zama matattara ga mutane da kuma aminci; kuma ku mayar da Maƙamu Ibrahim wajen salla; kuma Muka yi umarni ga Ibrahim da Isma'ila da cewa: "Ku tsarkake Ɗakina don masu ɗawafi da masu i'itikafi da masu ruku'u da sujjada"

(126) Kuma ka tuna lokacin da Ibrahimu ya ce: "Ya Ubangijina, Ka sanya wannan (wuri) ya zama gari mai aminci, kuma Ka arzuta mutanensa da kayan marmari, (amma) wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira daga cikinsu". Sai (Allah) Ya ce: "Har ma wanda ya kafirta, zan jiyar da shi daɗi kaɗan, sannan in tilasa masa shiga azabar wuta, tir da wannan makoma."

وَإِذْ يَرْفَعُ إِبْرَٰهِـۧمُ ٱلْقَوَاعِدَ مِنَ ٱلْبَيْتِ وَإِسْمَٰعِيلُ رَبَّنَا تَقَبَّلْ
مِنَّآ ۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ ﴿١٢٧﴾ رَبَّنَا وَٱجْعَلْنَا مُسْلِمَيْنِ
لَكَ وَمِن ذُرِّيَّتِنَآ أُمَّةً مُّسْلِمَةً لَّكَ وَأَرِنَا مَنَاسِكَنَا وَتُبْ عَلَيْنَآ ۖ
إِنَّكَ أَنتَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٢٨﴾ رَبَّنَا وَٱبْعَثْ فِيهِمْ رَسُولًا مِّنْهُمْ
يَتْلُوا۟ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتِكَ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ
وَيُزَكِّيهِمْ ۚ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿١٢٩﴾ وَمَن يَرْغَبُ عَن مِّلَّةِ
إِبْرَٰهِـۧمَ إِلَّا مَن سَفِهَ نَفْسَهُۥ ۚ وَلَقَدِ ٱصْطَفَيْنَٰهُ فِى ٱلدُّنْيَا ۖ
وَإِنَّهُۥ فِى ٱلْءَاخِرَةِ لَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿١٣٠﴾ إِذْ قَالَ لَهُۥ رَبُّهُۥٓ أَسْلِمْ ۖ
قَالَ أَسْلَمْتُ لِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٣١﴾ وَوَصَّىٰ بِهَآ إِبْرَٰهِـۧمُ بَنِيهِ
وَيَعْقُوبُ يَٰبَنِىَّ إِنَّ ٱللَّهَ ٱصْطَفَىٰ لَكُمُ ٱلدِّينَ فَلَا تَمُوتُنَّ
إِلَّا وَأَنتُم مُّسْلِمُونَ ﴿١٣٢﴾ أَمْ كُنتُمْ شُهَدَآءَ إِذْ حَضَرَ يَعْقُوبَ
ٱلْمَوْتُ إِذْ قَالَ لِبَنِيهِ مَا تَعْبُدُونَ مِنۢ بَعْدِى ۖ قَالُوا۟ نَعْبُدُ
إِلَٰهَكَ وَإِلَٰهَ ءَابَآئِكَ إِبْرَٰهِـۧمَ وَإِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ إِلَٰهًا
وَٰحِدًا وَنَحْنُ لَهُۥ مُسْلِمُونَ ﴿١٣٣﴾ تِلْكَ أُمَّةٌ قَدْ خَلَتْ ۖ لَهَا مَا كَسَبَتْ
وَلَكُم مَّا كَسَبْتُمْ ۖ وَلَا تُسْـَٔلُونَ عَمَّا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٣٤﴾



(127) Kuma ka tuna lokacin da Ibrahimu yake ɗaga harsashen ginin Dakin Ka'aba tare da Isma'ila, suna cewa: "Ya Ubangijinmu Ka karɓa mana; lalle Kai Mai ji ne Mai gani."

(128) "Ya Ubangijinmu, Ka sanya mu masu miƙa wuya gare Ka, kuma a cikin zurriyarmu ma (Ka samar) da wata al'umma mai miƙa wuya gare Ka, kuma Ka nuna mana ayyaukan ibadarmu, kuma Ka karɓi tubanmu, lalle Kai Mai yawan karɓar tuba ne Mai jin ƙai."

(129) "Ya Ubangijinmu, Ka aiko da wani manzo daga cikinsu, da zai riƙa karanta musu ayoyinka, kuma yana koyar da su Littafi da hikima, kuma ya riƙa yi musu tarbiyya. Lalle kai Mabuwayi ne, Mai hikima."

(130) Babu kuma wanda zai ƙi addinin Ibrahimu sai wanda bai san ciwon kansa ba. Kuma haƙiƙa Mun zaɓe shi a duniya, kuma shi a lahira yana cikin mutanen ƙwarai

(131) Ka tuna lokacin da Ubangijijinsa Ya ce masa: "Ka miƙa wuya", sai ya ce: "Na miƙa wuya ga Ubangijin talikai."

(132) Kuma Ibrahimu da Ya'aƙubu suka yi wasiyya da wannan ga 'ya'yansu cewa: "Ya 'ya'yana, lalle Allah Ya zaɓa muku addini, don haka kada ku mutu face kuna Musulmi."

(133) Ko kuna nan ne lokacin da mutuwa ta zo wa Ya'aƙubu, lokacin da ya ce wa 'ya'yansa: "Me za ku bauta wa a bayana?" Sai suka ce: "Za mu bauta wa abin bautarka kuma abin bautar iyayenka, Ibrahim da Isma'il da Ishaƙ, abin bauta guda ɗaya, kuma mu gare Shi muke miƙa wuya."

(134) Waccan al'umma ce da ta riga ta wuce; abin da ta aikata mallakarta ne, ku ma abin da kuka aikata naku ne, kuma ba za a tambaye ku ba game da abin da suka kasance suna aikatawa."

وَقَالُوا۟ كُونُوا۟ هُودًا أَوْ نَصَٰرَىٰ تَهْتَدُوا۟ ۗ قُلْ بَلْ مِلَّةَ إِبْرَٰهِـۧمَ
حَنِيفًا ۖ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿١٣٥﴾ قُولُوٓا۟ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ
أُنزِلَ إِلَيْنَا وَمَآ أُنزِلَ إِلَىٰٓ إِبْرَٰهِـۧمَ وَإِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ
وَٱلْأَسْبَاطِ وَمَآ أُوتِىَ مُوسَىٰ وَعِيسَىٰ وَمَآ أُوتِىَ ٱلنَّبِيُّونَ مِن
رَّبِّهِمْ لَا نُفَرِّقُ بَيْنَ أَحَدٍ مِّنْهُمْ وَنَحْنُ لَهُۥ مُسْلِمُونَ ﴿١٣٦﴾
فَإِنْ ءَامَنُوا۟ بِمِثْلِ مَآ ءَامَنتُم بِهِۦ فَقَدِ ٱهْتَدَوا۟ ۖ وَّإِن تَوَلَّوْا۟
فَإِنَّمَا هُمْ فِى شِقَاقٍ ۖ فَسَيَكْفِيكَهُمُ ٱللَّهُ ۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ
﴿١٣٧﴾ صِبْغَةَ ٱللَّهِ ۖ وَمَنْ أَحْسَنُ مِنَ ٱللَّهِ صِبْغَةً ۖ وَنَحْنُ لَهُۥ
عَٰبِدُونَ ﴿١٣٨﴾ قُلْ أَتُحَآجُّونَنَا فِى ٱللَّهِ وَهُوَ رَبُّنَا وَرَبُّكُمْ
وَلَنَآ أَعْمَٰلُنَا وَلَكُمْ أَعْمَٰلُكُمْ وَنَحْنُ لَهُۥ مُخْلِصُونَ ﴿١٣٩﴾
أَمْ تَقُولُونَ إِنَّ إِبْرَٰهِـۧمَ وَإِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ
وَٱلْأَسْبَاطَ كَانُوا۟ هُودًا أَوْ نَصَٰرَىٰ ۗ قُلْ ءَأَنتُمْ أَعْلَمُ أَمِ
ٱللَّهُ ۗ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن كَتَمَ شَهَٰدَةً عِندَهُۥ مِنَ ٱللَّهِ ۗ وَمَا ٱللَّهُ
بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿١٤٠﴾ تِلْكَ أُمَّةٌ قَدْ خَلَتْ ۖ لَهَا مَا كَسَبَتْ
وَلَكُم مَّا كَسَبْتُمْ ۖ وَلَا تُسْـَٔلُونَ عَمَّا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٤١﴾

(135) Kuma suka ce: “Ku zama Yahudawa ko Nasara za ku shiriya”. Ka ce: “A’a! (Za mu bi) addinin Ibrahimu ne wanda yake miƙe totar, kuma bai zamo daga cikin masu shirka ba.”

(136) Ku ce: “Mun yi imani da Allah da abin da aka saukar mana, da abin da aka saukar wa Ibrahimu da Isma’ila da Ishaƙa da Ya’aƙubu da jikoki da abin da aka ba wa Musa da Isa da abin da aka ba annabawa duka daga Ubangijinsu, kuma ba ma nuna bambanci tsakanin wani daga cikinsu, kuma mu gare Shi muke miƙa wuya.”


(137) Don haka idan sun yi imani da irin abin da kuka yi imani da shi, to haƙiƙa sun shiriya, idan kuwa suka juya da baya, to haƙiƙa su suna cikin saɓani. To da sannu Allah zai isar maka da su, kuma Shi Mai ji ne, Mai gani

(138) Rinin Allah, wane ne kuwa ya fi Allah kyan rini? Kuma mu masu bauta ne a gare Shi

(139) Ka ce, “Shin za ku yi jayayya da mu ne game da sha’anin Allah, alhalin Shi ne Ubangijinmu kuma Ubangijinku? Kuma ayyukanmu namu ne, ayyukanku kuma naku ne, kuma mu masu tsarkake ayyuka ne gare Shi (Allah)

(140) Ko kuma kuna cewa ne, “Lalle Ibrahimu da Isma’ila da Ishaƙa da Ya’aƙubu da jikoki sun kasance Yahudawa ne ko Nasara?” Ka ce: “Ku ne kuka fi sani ko kuma Allah?” Kuma ba wanda ya fi zalunci kamar wanda ya ɓoye shaidar da take wajensa daga Allah, kuma Allah ba rafkananne ne ba game da abin da kuke aikatawa

(141) Waccan al’umma ce da ta riga ta wuce, abin da ta aikata mallakarta ne, ku ma abin da kuka aikata naku ne, kuma ba za a tambaye ku game da abin da suka kasance suna aikatawa ba.”


* سَيَقُولُ ٱلسُّفَهَآءُ مِنَ ٱلنَّاسِ مَا وَلَّىٰهُمْ عَن قِبْلَتِهِمُ ٱلَّتِى كَانُوا۟
عَلَيْهَا ۚ قُل لِّلَّهِ ٱلْمَشْرِقُ وَٱلْمَغْرِبُ ۚ يَهْدِى مَن يَشَآءُ إِلَىٰ صِرَٰطٍ
مُّسْتَقِيمٍ ﴿١٤٢﴾ وَكَذَٰلِكَ جَعَلْنَٰكُمْ أُمَّةً وَسَطًا لِّتَكُونُوا۟
شُهَدَآءَ عَلَى ٱلنَّاسِ وَيَكُونَ ٱلرَّسُولُ عَلَيْكُمْ شَهِيدًا ۗ وَمَا
جَعَلْنَا ٱلْقِبْلَةَ ٱلَّتِى كُنتَ عَلَيْهَآ إِلَّا لِنَعْلَمَ مَن يَتَّبِعُ ٱلرَّسُولَ
مِمَّن يَنقَلِبُ عَلَىٰ عَقِبَيْهِ ۚ وَإِن كَانَتْ لَكَبِيرَةً إِلَّا عَلَى ٱلَّذِينَ
هَدَى ٱللَّهُ ۗ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُضِيعَ إِيمَٰنَكُمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ
بِٱلنَّاسِ لَرَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿١٤٣﴾ قَدْ نَرَىٰ تَقَلُّبَ وَجْهِكَ فِى ٱلسَّمَآءِ ۖ
فَلَنُوَلِّيَنَّكَ قِبْلَةً تَرْضَىٰهَا ۚ فَوَلِّ وَجْهَكَ شَطْرَ ٱلْمَسْجِدِ
ٱلْحَرَامِ ۚ وَحَيْثُ مَا كُنتُمْ فَوَلُّوا۟ وُجُوهَكُمْ شَطْرَهُۥ ۗ وَإِنَّ
ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ لَيَعْلَمُونَ أَنَّهُ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّهِمْ ۗ وَمَا ٱللَّهُ
بِغَٰفِلٍ عَمَّا يَعْمَلُونَ ﴿١٤٤﴾ وَلَئِنْ أَتَيْتَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ
بِكُلِّ ءَايَةٍ مَّا تَبِعُوا۟ قِبْلَتَكَ ۚ وَمَآ أَنتَ بِتَابِعٍ قِبْلَتَهُمْ ۚ
وَمَا بَعْضُهُم بِتَابِعٍ قِبْلَةَ بَعْضٍ ۚ وَلَئِنِ ٱتَّبَعْتَ أَهْوَآءَهُم مِّنۢ
بَعْدِ مَا جَآءَكَ مِنَ ٱلْعِلْمِ ۙ إِنَّكَ إِذًا لَّمِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٤٥﴾

(142) Ba da jimawa ba wawayen mutane za su ce: “Mene ne ya sa su juyawa su bar alƙibilar da a da suke a kanta?”(1) Ka ce: “Gabas da yamma na Allah ne, Yana shiryar da wanda Ya ga dama zuwa ga tafarki madaidaici.”

(143) Kamar haka ne Muka sanya ku al’umma tsaka-tsaki (zaɓaɓɓu) don ku zamo masu shaida ga mutane, kuma Manzo ya zamo mai shaida a gare ku. Kuma ba Mu sanya alƙiblar da ka kasance a kanta ba sai don Mu bayyana wanda yake biyayya ga Manzo da wanda zai ja da baya (ya bijire). Kuma lalle wannan babban lamari ne sai dai ga waɗanda Allah Ya shiryar. Kuma Allah ba zai taɓa tozarta imaninku ba. Lalle Allah Mai tausayi ne, Mai jin ƙai ga mutane

(144) Haƙiƙa Mun ga jujjuyawar fuskarka zuwa sama, to lalle za Mu fuskantar da kai zuwa ga alƙibilar da za ka yarda da ita. Don haka ka juyar da fuskarka wajajen Masallaci mai alfarma; ku ma (Musulmi) a duk inda kuke to ku juyar da fuskokinku wajajensa. Lalle kuma waɗanda aka ba su Littafi suna sane da cewa, lalle shi (wannan canji) gaskiya ne daga Ubangijinsu. Kuma Allah ba rafkananne ba ne game da abin da suke aikatawa

(145) Lalle kuma da za ka kawo wa waɗanda aka ba su Littafi kowace irin hujja ba za su bi alƙibilarka ba; kuma kai ma ba mai bin alƙibilarsu ba ne; kuma sashinsu bai zama mai bin alƙibilar sashi ba. Kuma haƙiƙa idan har ka bi soye-soyen zukatansu bayan abin da ya zo maka na gaskiya, to lalle idan ka yi haka tabbas kana cikin azzalumai

(1) Kafin saukar aya ta 144, Annabi ( ) da sahabbansa a Makka suna fuskantar Baitul Maƙdis yayin sallolinsu. Bayan sun yi hijira zuwa Madina sai Allah ya canza musu alƙibla zuwa Ka’aba. Daga nan ne Yahudawa da Mushirikan Larabwa suka samu abin magana.

ٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ يَعۡرِفُونَهُۥ كَمَا يَعۡرِفُونَ أَبۡنَآءَهُمۡۖ
وَإِنَّ فَرِيقٗا مِّنۡهُمۡ لَيَكۡتُمُونَ ٱلۡحَقَّ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ١٤٦ ٱلۡحَقُّ
مِن رَّبِّكَ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡمُمۡتَرِينَ ١٤٧ وَلِكُلّٖ وِجۡهَةٌ
هُوَ مُوَلِّيهَاۖ فَٱسۡتَبِقُواْ ٱلۡخَيۡرَٰتِۚ أَيۡنَ مَا تَكُونُواْ يَأۡتِ بِكُمُ ٱللَّهُ
جَمِيعًاۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ١٤٨ وَمِنۡ حَيۡثُ خَرَجۡتَ
فَوَلِّ وَجۡهَكَ شَطۡرَ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِۖ وَإِنَّهُۥ لَلۡحَقُّ مِن رَّبِّكَۗ
وَمَا ٱللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ١٤٩ وَمِنۡ حَيۡثُ خَرَجۡتَ فَوَلِّ
وَجۡهَكَ شَطۡرَ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِۚ وَحَيۡثُ مَا كُنتُمۡ فَوَلُّواْ
وُجُوهَكُمۡ شَطۡرَهُۥ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَيۡكُمۡ حُجَّةٌ إِلَّا ٱلَّذِينَ
ظَلَمُواْ مِنۡهُمۡ فَلَا تَخۡشَوۡهُمۡ وَٱخۡشَوۡنِي وَلِأُتِمَّ نِعۡمَتِي عَلَيۡكُمۡ
وَلَعَلَّكُمۡ تَهۡتَدُونَ ١٥٠ كَمَآ أَرۡسَلۡنَا فِيكُمۡ رَسُولٗا مِّنكُمۡ يَتۡلُواْ
عَلَيۡكُمۡ ءَايَٰتِنَا وَيُزَكِّيكُمۡ وَيُعَلِّمُكُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ
وَيُعَلِّمُكُم مَّا لَمۡ تَكُونُواْ تَعۡلَمُونَ ١٥١ فَٱذۡكُرُونِيٓ أَذۡكُرۡكُمۡ
وَٱشۡكُرُواْ لِي وَلَا تَكۡفُرُونِ ١٥٢ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
ٱسۡتَعِينُواْ بِٱلصَّبۡرِ وَٱلصَّلَوٰةِۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٥٣

(146) Waɗanda Muka ba su Littafi suna sane da shi (Manzon Allah) kamar yadda suke sane da ‘ya’yansu; kuma lalle wani ɓangare daga cikinsu tabbas suna ɓoye gaskiya alhalin suna sane

(147) Gaskiya kam daga Ubangijinka take, don haka lalle kada ka zama daga cikin masu shakka

(148) Kuma kowane ɓangare yana da inda ya sa gaba, don haka sai ku yi gaggawar cim ma alheri. A duk inda kuke Allah zai zo da ku gaba ɗaya. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai

(149) Ko ta ina ka fito, to ka juyar da fuskarka wajajen Masallaci mai alfarma; kuma lalle shi gaskiya ne daga Ubangijinka. Kuma Allah bai zama gafalalle game da abin da kuke aikatawa ba

(150) Kuma duk inda ka fita, to ka juyar da fuskarka wajajen Masallaci mai alfarma. Ku ma duk inda kuke to ku juyar da fuskokinku wajajensa, don kada ya zama mutane suna da wata hujja a kanku, sai dai waɗanda suka yi zalunci daga cikinsu, don haka kada ku ji tsoron su, ku ji tsorona, kuma domin in cika muku ni’imata, don ku shiriya

(151) Kamar yadda Muka aiko muku da wani manzo daga cikinku, yana karanta muku ayoyinmu, kuma yana tsarkake ku, kuma yana koyar da ku Littafi da Hikima(1), kuma yana koyar da ku abin da a da can ba ku sani ba

(152) Don haka ku ambace Ni, Ni ma zan ambace ku, kuma ku gode Mini, kada kuma ku kafirce Mini

(153) Ya ku waɗanda suka yi imani ku nemi taimako ta hanyar haƙuri da salla. Lalle Allah Yana tare da masu haƙuri

(1) Hikima, ita ce sunnar Annabi ( ).

وَلَا تَقُولُوا۟ لِمَن يُقْتَلُ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ أَمْوَٰتٌۢ ۚ بَلْ أَحْيَآءٌ وَلَٰكِن
لَّا تَشْعُرُونَ ﴿١٥٤﴾ وَلَنَبْلُوَنَّكُم بِشَىْءٍ مِّنَ ٱلْخَوْفِ وَٱلْجُوعِ
وَنَقْصٍ مِّنَ ٱلْأَمْوَٰلِ وَٱلْأَنفُسِ وَٱلثَّمَرَٰتِ ۗ وَبَشِّرِ ٱلصَّٰبِرِينَ ﴿١٥٥﴾
ٱلَّذِينَ إِذَآ أَصَٰبَتْهُم مُّصِيبَةٌ قَالُوٓا۟ إِنَّا لِلَّهِ وَإِنَّآ إِلَيْهِ رَٰجِعُونَ
﴿١٥٦﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ عَلَيْهِمْ صَلَوَٰتٌ مِّن رَّبِّهِمْ وَرَحْمَةٌ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ
هُمُ ٱلْمُهْتَدُونَ ﴿١٥٧﴾ ۞ إِنَّ ٱلصَّفَا وَٱلْمَرْوَةَ مِن شَعَآئِرِ ٱللَّهِ ۖ
فَمَنْ حَجَّ ٱلْبَيْتَ أَوِ ٱعْتَمَرَ فَلَا جُنَاحَ عَلَيْهِ أَن يَطَّوَّفَ بِهِمَا ۚ
وَمَن تَطَوَّعَ خَيْرًا فَإِنَّ ٱللَّهَ شَاكِرٌ عَلِيمٌ ﴿١٥٨﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ
يَكْتُمُونَ مَآ أَنزَلْنَا مِنَ ٱلْبَيِّنَٰتِ وَٱلْهُدَىٰ مِنۢ بَعْدِ مَا بَيَّنَّٰهُ
لِلنَّاسِ فِى ٱلْكِتَٰبِ ۙ أُو۟لَٰٓئِكَ يَلْعَنُهُمُ ٱللَّهُ وَيَلْعَنُهُمُ ٱللَّٰعِنُونَ
﴿١٥٩﴾ إِلَّا ٱلَّذِينَ تَابُوا۟ وَأَصْلَحُوا۟ وَبَيَّنُوا۟ فَأُو۟لَٰٓئِكَ أَتُوبُ عَلَيْهِمْ
وَأَنَا ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٦٠﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَمَاتُوا۟ وَهُمْ
كُفَّارٌ أُو۟لَٰٓئِكَ عَلَيْهِمْ لَعْنَةُ ٱللَّهِ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلنَّاسِ أَجْمَعِينَ
﴿١٦١﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۖ لَا يُخَفَّفُ عَنْهُمُ ٱلْعَذَابُ وَلَا هُمْ يُنظَرُونَ ﴿١٦٢﴾
وَإِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ ۖ لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلرَّحْمَٰنُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٦٣﴾

(154) Kada kuma ku ce wa waɗanda ake kashewa a kan hanyar Allah su matattu ne. A'a, rayayyu ne, sai dai ku ne ba ku sani ba

(155) Kuma lalle za Mu jarrabe ku da wani abin tsoro da yunwa da tawayar dukiya da ta rayuka da ta 'ya'yan itatuwa. Don haka ka yi albishir ga masu haƙuri

(156) (Su ne) waɗanda idan wata musiba ta same su sai su ce: "Lalle mu na Allah ne, kuma lalle mu gare Shi muke komawa."

(157) Waɗannan suna da yabo daga Ubangijinsu da rahama, kuma waɗannan su ne shiryayyu

(158) Lalle dutsen Safa da na Marwa suna cikin alamomin bautar Allah, don haka wanda ya je Hajji ga Ɗakin Allah ko ya je Umara, to babu wani laifi a gare shi ya yi ɗawafi tsakaninsu. Kuma wanda ya yi biyayya ta hanyar aikata alheri, to lalle Allah Mai godiya ne kuma Masani

(159) Lalle waɗanda suke ɓoye abin da Muka saukar na hujjoji da shiriya bayan Mun yi bayanin su ga mutane a cikin Littafi, to waɗannan su ne Allah Yake la'antar su, kuma masu la'anta su ma suke la'antar su

(160) Sai dai waɗanda suka tuba kuma suka gyara kuma suka bayyana, to waɗannan zan karɓi tubansu, kuma lalle Ni Mai karɓar tuba ne, Mai jin ƙai

(161) Lalle waɗanda suka kafirta kuma suka mutu suna kafirai, to waɗannan la'anar Allah ta tabbata a kansu da ta mala'iku da mutane gaba ɗaya

(162) Suna masu dawwama a cikinta, ba za a sassauta masu azaba ba kuma ba za a saurara musu ba

(163) Kuma abin bautarku abin bauta ne Guda Ɗaya, babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. Shi ne Mai rahama, Mai jin ƙai

إِنَّ فِي خَلْقِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَٱخْتِلَٰفِ ٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ
وَٱلْفُلْكِ ٱلَّتِي تَجْرِي فِي ٱلْبَحْرِ بِمَا يَنفَعُ ٱلنَّاسَ وَمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ
مِنَ ٱلسَّمَآءِ مِن مَّآءٍ فَأَحْيَا بِهِ ٱلْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا وَبَثَّ فِيهَا
مِن كُلِّ دَآبَّةٍ وَتَصْرِيفِ ٱلرِّيَٰحِ وَٱلسَّحَابِ ٱلْمُسَخَّرِ بَيْنَ
ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ﴿١٦٤﴾ وَمِنَ ٱلنَّاسِ
مَن يَتَّخِذُ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَندَادًا يُحِبُّونَهُمْ كَحُبِّ ٱللَّهِ ۖ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُوٓا۟ أَشَدُّ حُبًّا لِّلَّهِ ۗ وَلَوْ يَرَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓا۟ إِذْ يَرَوْنَ
ٱلْعَذَابَ أَنَّ ٱلْقُوَّةَ لِلَّهِ جَمِيعًا وَأَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعَذَابِ ﴿١٦٥﴾
إِذْ تَبَرَّأَ ٱلَّذِينَ ٱتُّبِعُوا۟ مِنَ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوا۟ وَرَأَوُا۟ ٱلْعَذَابَ
وَتَقَطَّعَتْ بِهِمُ ٱلْأَسْبَابُ ﴿١٦٦﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوا۟ لَوْ أَنَّ
لَنَا كَرَّةً فَنَتَبَرَّأَ مِنْهُمْ كَمَا تَبَرَّءُوا۟ مِنَّا ۗ كَذَٰلِكَ يُرِيهِمُ ٱللَّهُ
أَعْمَٰلَهُمْ حَسَرَٰتٍ عَلَيْهِمْ ۖ وَمَا هُم بِخَٰرِجِينَ مِنَ ٱلنَّارِ ﴿١٦٧﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ كُلُوا۟ مِمَّا فِي ٱلْأَرْضِ حَلَٰلًا طَيِّبًا وَلَا تَتَّبِعُوا۟
خُطُوَٰتِ ٱلشَّيْطَٰنِ ۚ إِنَّهُۥ لَكُمْ عَدُوٌّ مُّبِينٌ ﴿١٦٨﴾ إِنَّمَا يَأْمُرُكُم
بِٱلسُّوٓءِ وَٱلْفَحْشَآءِ وَأَن تَقُولُوا۟ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿١٦٩﴾

(164) Lalle a cikin halittar sammai da ƙasa da sassaɓawar dare da rana da jiragen ruwa da suke tafiya a kan ruwa da abin da yake amfanar mutane da kuma abin da Allah Ya saukar daga sama na ruwa, Ya rayar da ƙasa da shi bayan mutuwarta, Ya kuma yaɗa duk wata halitta mai tafiya a cikin (ƙasa) da jujjuyawar iska, da kuma girgije da aka hore shi tsakanin sama da ƙasa, lalle akwai ayoyi ga mutane masu hankali

(165) Kuma akwai wasu mutane waɗanda suke bauta wa wasu kishiyoyi ba Allah ba; suna son su kamar son Allah; waɗanda kuwa suka yi imani sun fi son Allah (fiye da komai). Da a ce waɗanda suka yi zalunci za su ga lokacin da suke ido huɗu da azaba (to da sun gane) cewa, lalle duk wani ƙarfi na Allah ne gaba ɗaya, kuma lalle Allah Mai tsananin azaba ne

(166) Lokacin da waɗanda aka yi wa biyayya (shugabanni) za su nisantar da kansu daga waɗanda suka yi musu biyayya (mabiya), kuma suka yi arba da azaba, kuma duk wasu alaƙoƙi da ke tsakaninsu suka yanke


(167) Kuma waɗanda suka yi biyayya suka ce: "Ina ma dai muna da wata dama ta komawa (duniya) don mu ma mu nisantar da kanmu daga gare su, kamar yadda suka nisanta kansu daga gare mu?" Kamar haka ne Allah Yake nuna musu ayyukansu suka zama nadama a gare su, kuma su ba masu samun fita ne daga wuta ba

(168) Ya ku mutane, ku ci halal mai daɗi na abin da ke bayan ƙasa, kada kuma ku bi hanyoyin Shaiɗan, lalle shi maƙiyi ne mai bayyana ƙiyayya a gare ku

(169) Yana umartar ku ne kawai da saɓo da ayyukan assha da kuma faɗin abin da ba ku da ilimi game da shi ku jingina wa Allah

وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱتَّبِعُوا۟ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ قَالُوا۟ بَلْ نَتَّبِعُ مَآ أَلْفَيْنَا
عَلَيْهِ ءَابَآءَنَآ ۚ أَوَلَوْ كَانَ ءَابَآؤُهُمْ لَا يَعْقِلُونَ شَيْـًٔا وَلَا
يَهْتَدُونَ ﴿١٧٠﴾ وَمَثَلُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ كَمَثَلِ ٱلَّذِى يَنْعِقُ
بِمَا لَا يَسْمَعُ إِلَّا دُعَآءً وَنِدَآءً ۚ صُمٌّۢ بُكْمٌ عُمْىٌ فَهُمْ لَا يَعْقِلُونَ
﴿١٧١﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ كُلُوا۟ مِن طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقْنَٰكُمْ
وَٱشْكُرُوا۟ لِلَّهِ إِن كُنتُمْ إِيَّاهُ تَعْبُدُونَ ﴿١٧٢﴾ إِنَّمَا حَرَّمَ
عَلَيْكُمُ ٱلْمَيْتَةَ وَٱلدَّمَ وَلَحْمَ ٱلْخِنزِيرِ وَمَآ أُهِلَّ بِهِۦ لِغَيْرِ
ٱللَّهِ ۖ فَمَنِ ٱضْطُرَّ غَيْرَ بَاغٍ وَلَا عَادٍ فَلَآ إِثْمَ عَلَيْهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ
غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٧٣﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكْتُمُونَ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ مِنَ
ٱلْكِتَٰبِ وَيَشْتَرُونَ بِهِۦ ثَمَنًا قَلِيلًا أُو۟لَٰٓئِكَ مَا يَأْكُلُونَ
فِى بُطُونِهِمْ إِلَّا ٱلنَّارَ وَلَا يُكَلِّمُهُمُ ٱللَّهُ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ
وَلَا يُزَكِّيهِمْ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿١٧٤﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ
ٱشْتَرَوُا۟ ٱلضَّلَٰلَةَ بِٱلْهُدَىٰ وَٱلْعَذَابَ بِٱلْمَغْفِرَةِ ۚ فَمَآ
أَصْبَرَهُمْ عَلَى ٱلنَّارِ ﴿١٧٥﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ نَزَّلَ ٱلْكِتَٰبَ بِٱلْحَقِّ ۗ
وَإِنَّ ٱلَّذِينَ ٱخْتَلَفُوا۟ فِى ٱلْكِتَٰبِ لَفِى شِقَاقٍۭ بَعِيدٍ ﴿١٧٦﴾

(170) Idan kuma aka ce musu: “Ku bi abin da Allah Ya saukar”, sai su ce: “A’a, za dai mu bi abin da muka samu iyayenmu a kansa”. To, ko da iyayensu ba sa hankaltar komai, kuma ba sa shiryuwa?
(171) Misalin wadanda suka kafirta kamar misalin wanda yake daga sauti ne ga wanda ba ya jin (komai) sai kira da sowa. Kurame ne, bebaye ne, makafi ne, don haka su ba sa hankalta
(172) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ci daga daɗaɗan abin da Muka arzuta ku (da shi), kuma ku yi godiya ga Allah in har kun kasance Shi kaɗai kuke bauta wa
(173) (Allah) Ya haramta muku mushe ne kawai da jini da naman alade da abin da aka kira sunan wani ba Allah ba (lokacin yanka shi). Don haka duk wanda ya matsu, ba mai zalunci ba, kuma ba mai ƙetare iyaka ba, to babu laifi a kansa ya ci. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai
(174) Lalle waɗanda suke ɓoye abin da Allah Ya saukar na Littafi, kuma suke musanya shi da ɗan kuɗi kaɗan, waɗannan babu abin da suke ci a cikkunansu sai wuta, kuma Allah ba zai yi musu magana ba ranar tashin alƙiyama, kuma ba zai tsarkake su ba, kuma suna da wata azaba mai raɗaɗi
(175) Waɗannan su ne waɗanda suka zaɓi ɓata a madadin shiriya da kuma azaba a madadin gafara. Don haka yi mamakin haƙurin (zamansu) a cikin wuta
(176) Wannan ya faru ne saboda lalle Allah Ya saukar da Littafinsa da gaskiya. Kuma lalle duk waɗanda suka yi saɓani dangane da Littafin, tabbas suna cikin saɓawa mai nisa


لَّيْسَ ٱلْبِرَّ أَن تُوَلُّوا۟ وُجُوهَكُمْ قِبَلَ ٱلْمَشْرِقِ وَٱلْمَغْرِبِ
وَلَٰكِنَّ ٱلْبِرَّ مَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةِ
وَٱلْكِتَٰبِ وَٱلنَّبِيِّۦنَ وَءَاتَى ٱلْمَالَ عَلَىٰ حُبِّهِۦ ذَوِى ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ
وَٱلْمَسَٰكِينَ وَٱبْنَ ٱلسَّبِيلِ وَٱلسَّآئِلِينَ وَفِى ٱلرِّقَابِ وَأَقَامَ
ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَى ٱلزَّكَوٰةَ وَٱلْمُوفُونَ بِعَهْدِهِمْ إِذَا عَٰهَدُوا۟ ۖ
وَٱلصَّٰبِرِينَ فِى ٱلْبَأْسَآءِ وَٱلضَّرَّآءِ وَحِينَ ٱلْبَأْسِ ۗ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ
صَدَقُوا۟ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُتَّقُونَ ﴿١٧٧﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ كُتِبَ
عَلَيْكُمُ ٱلْقِصَاصُ فِى ٱلْقَتْلَى ۖ ٱلْحُرُّ بِٱلْحُرِّ وَٱلْعَبْدُ بِٱلْعَبْدِ وَٱلْأُنثَىٰ
بِٱلْأُنثَىٰ ۚ فَمَنْ عُفِىَ لَهُۥ مِنْ أَخِيهِ شَىْءٌ فَٱتِّبَاعٌۢ بِٱلْمَعْرُوفِ وَأَدَآءٌ
إِلَيْهِ بِإِحْسَٰنٍ ۗ ذَٰلِكَ تَخْفِيفٌ مِّن رَّبِّكُمْ وَرَحْمَةٌ ۗ فَمَنِ ٱعْتَدَىٰ
بَعْدَ ذَٰلِكَ فَلَهُۥ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿١٧٨﴾ وَلَكُمْ فِى ٱلْقِصَاصِ حَيَوٰةٌ يَٰٓأُو۟لِى
ٱلْأَلْبَٰبِ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿١٧٩﴾ كُتِبَ عَلَيْكُمْ إِذَا حَضَرَ
أَحَدَكُمُ ٱلْمَوْتُ إِن تَرَكَ خَيْرًا ٱلْوَصِيَّةُ لِلْوَٰلِدَيْنِ وَٱلْأَقْرَبِينَ
بِٱلْمَعْرُوفِ ۖ حَقًّا عَلَى ٱلْمُتَّقِينَ ﴿١٨٠﴾ فَمَنۢ بَدَّلَهُۥ بَعْدَ مَا سَمِعَهُۥ
فَإِنَّمَآ إِثْمُهُۥ عَلَى ٱلَّذِينَ يُبَدِّلُونَهُۥٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿١٨١﴾

(177) Ba wai aikin ɗa'a shi ne ku juyar da fuskokinku mahudar rana ko mafaɗarta ba ; sai dai aikin ɗa'a shi ne, wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira da mala'iku da littattafai da annabawa, kuma ya bayar da dukiyarsa, alhalin yana son ta, ga dangi na kusa da marayu da mabuƙata da matafiyi da kuma masu roƙo (bisa larura) da 'yantar da bayi, sannan kuma ya tsayar da salla, kuma ya bayar da zakka, da kuma masu cika alƙawarinsu idan suka ƙulla alƙawari ; da masu haƙuri a cikin halin talauci da halin rashin lafiya da lokacin yaƙi. Waɗannan su ne waɗanda suka yi gaskiya, kuma waɗannan su ne masu taƙawa

(178) Ya ku waɗanda suka yi imani, an wajabta muku ƙisasi dangane da waɗanda aka kashe; ɗa da ɗa, bawa da bawa, mace da mace[1]. To duk wanda aka yafe masa ƙisasin ɗan uwansa, to sai ya bibiye shi ta hanyar da ta dace, shi kuma ya biya diyyar ta hanyar kyautatawa. Wannan (abin da aka ambata), sauƙi ne da rahama daga wajen Ubangijinku. Don haka duk wanda ya ƙetare iyaka bayan haka, to yana da azaba mai raɗaɗi

(179) Kuma a cikin (hukuncin) ƙisasi akwai (tsare) rayuwa a gare ku, ya ku ma'abota hankula, don ku samu taƙawa

(180) An wajabta muku, idan alamun mutuwa suka zo wa ɗayanku, idan har ya bar wani alheri (dukiya), to ya yi wasiyya ga mahaifa biyu da dangi mafiya kusanci, ta hanyar da ta dace (a shari'a). Haƙƙi ne tabbatacce a kan masu taƙawa[2]

(181) To wanda ya canza shi (lamarin wasiyya) bayan ya ji shi, to lalle laifinsa yana kan waɗanda suka canza shi ne kawai. Lalle Allah Mai ji ne, Masani

(1) Haka hukuncin yake yayin da namiji ɗa ya kashe 'ya mace, ko mace ta kashe ɗa namiji. Amma idan magadan wanda aka kashe suka yafe, to babu zancen ƙisasi, sai a biya diyya kawai.

(2) Wasu malamai suna ganin cewa, ayar rabon gado ta Suratun Nisa'i aya ta 11 ta shafe hukuncin wannan ayar. Wasu kuma suna ganin hukuncinta dangane da wasiyya ga makusanta da ba za su ci gado ba yana nan, amma da sharaɗin kada wasiyyar ta wuce sulusin abin da ya bari na dukiya.

فَمَنْ خَافَ مِن مُّوصٍ جَنَفًا أَوْ إِثْمًا فَأَصْلَحَ بَيْنَهُمْ فَلَآ إِثْمَ
عَلَيْهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٨٢﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ كُتِبَ
عَلَيْكُمُ ٱلصِّيَامُ كَمَا كُتِبَ عَلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ
لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿١٨٣﴾ أَيَّامًا مَّعْدُودَٰتٍ ۚ فَمَن كَانَ
مِنكُم مَّرِيضًا أَوْ عَلَىٰ سَفَرٍ فَعِدَّةٌ مِّنْ أَيَّامٍ أُخَرَ ۚ وَعَلَى
ٱلَّذِينَ يُطِيقُونَهُۥ فِدْيَةٌ طَعَامُ مِسْكِينٍ ۖ فَمَن تَطَوَّعَ خَيْرًا
فَهُوَ خَيْرٌ لَّهُۥ ۚ وَأَن تَصُومُوا۟ خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ
﴿١٨٤﴾ شَهْرُ رَمَضَانَ ٱلَّذِىٓ أُنزِلَ فِيهِ ٱلْقُرْءَانُ هُدًى لِّلنَّاسِ
وَبَيِّنَٰتٍ مِّنَ ٱلْهُدَىٰ وَٱلْفُرْقَانِ ۚ فَمَن شَهِدَ مِنكُمُ
ٱلشَّهْرَ فَلْيَصُمْهُ ۖ وَمَن كَانَ مَرِيضًا أَوْ عَلَىٰ سَفَرٍ فَعِدَّةٌ
مِّنْ أَيَّامٍ أُخَرَ ۗ يُرِيدُ ٱللَّهُ بِكُمُ ٱلْيُسْرَ وَلَا يُرِيدُ بِكُمُ
ٱلْعُسْرَ وَلِتُكْمِلُوا۟ ٱلْعِدَّةَ وَلِتُكَبِّرُوا۟ ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا
هَدَىٰكُمْ وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿١٨٥﴾ وَإِذَا سَأَلَكَ
عِبَادِى عَنِّى فَإِنِّى قَرِيبٌ ۖ أُجِيبُ دَعْوَةَ ٱلدَّاعِ إِذَا دَعَانِ ۖ
فَلْيَسْتَجِيبُوا۟ لِى وَلْيُؤْمِنُوا۟ بِى لَعَلَّهُمْ يَرْشُدُونَ ﴿١٨٦﴾

(182) To duk wanda ya ji tsoron kaucewa bisa kuskure ko bisa zalunci daga mai yin wasiyya sai ya sasanta tsakaninsu (mai wasiyyar da waɗanda aka yi wa wasiyyar); to wannan babu laifi a kansa; lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(183) Ya ku waɗanda suka yi imani, an wajabta muku azumi kamar yadda aka wajabta wa waɗanda suke gabaninku, don ku samu taƙawa

(184) Waɗansu kwanaki ne ƙididdigaggu. To duk wanda ya kasance marar lafiya a cikinku ko a kan wata tafiya, to (idan ya sha azumi) sai ya rama a waɗansu kwanakin na daban. Kuma waɗanda za su yi azumi da wahala su ba da fansa ta ciyar da miskini; to duk wanda ƙara (a kan abincin miskini), to wannan alheri ne gare shi. Amma ku yi azumin shi ne ya fi muku alheri, in har kun kusance kuna sani

(185) Watan Ramadan shi ne wanda aka saukar da Alƙur'ani a cikinsa, shiriya ne ga mutane kuma ayoyi ne bayyanannu na shiriya, kuma mai rarrabewa (tsakanin ƙarya da gaskiya). Don haka duk wanda ya halarci wannan watan daga cikinku, to ya azumce shi, kuma wanda ya kasance marar lafiya ko a kan wata tafiya, to (idan ya sha azumi) sai ya rama a waɗansu kwanakin na daban. Allah Yana nufin sauƙi a gare ku, kuma ba Ya nufin tsanani a gare ku, don ku cika adadin (kwanakin Ramadan), kuma domin ku girmama Allah bisa ga shiryar da ku da Ya yi, don ku yi godiya

(186) Kuma idan bayina sun tambaye ka game da Ni, to Ni kusa Nake (da su), Ina amsa kiran mai kira idan ya kiraye Ni; to su amsa Mini nawa kiran, kuma su yi imani da Ni, don su shiryu

أُحِلَّ لَكُمْ لَيْلَةَ ٱلصِّيَامِ ٱلرَّفَثُ إِلَىٰ نِسَآئِكُمْ ۚ هُنَّ
لِبَاسٌ لَّكُمْ وَأَنتُمْ لِبَاسٌ لَّهُنَّ ۗ عَلِمَ ٱللَّهُ أَنَّكُمْ كُنتُمْ
تَخْتَانُونَ أَنفُسَكُمْ فَتَابَ عَلَيْكُمْ وَعَفَا عَنكُمْ ۖ فَٱلْـَٰٔنَ
بَـٰشِرُوهُنَّ وَٱبْتَغُوا۟ مَا كَتَبَ ٱللَّهُ لَكُمْ ۚ وَكُلُوا۟ وَٱشْرَبُوا۟
حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَكُمُ ٱلْخَيْطُ ٱلْأَبْيَضُ مِنَ ٱلْخَيْطِ ٱلْأَسْوَدِ مِنَ
ٱلْفَجْرِ ۖ ثُمَّ أَتِمُّوا۟ ٱلصِّيَامَ إِلَى ٱلَّيْلِ ۚ وَلَا تُبَـٰشِرُوهُنَّ وَأَنتُمْ
عَـٰكِفُونَ فِى ٱلْمَسَـٰجِدِ ۗ تِلْكَ حُدُودُ ٱللَّهِ فَلَا تَقْرَبُوهَا ۗ كَذَٰلِكَ
يُبَيِّنُ ٱللَّهُ ءَايَـٰتِهِۦ لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ ﴿١٨٧﴾ وَلَا تَأْكُلُوٓا۟
أَمْوَٰلَكُم بَيْنَكُم بِٱلْبَـٰطِلِ وَتُدْلُوا۟ بِهَآ إِلَى ٱلْحُكَّامِ
لِتَأْكُلُوا۟ فَرِيقًا مِّنْ أَمْوَٰلِ ٱلنَّاسِ بِٱلْإِثْمِ وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ
﴿١٨٨﴾ ۞ يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْأَهِلَّةِ ۖ قُلْ هِىَ مَوَٰقِيتُ لِلنَّاسِ وَٱلْحَجِّ ۗ
وَلَيْسَ ٱلْبِرُّ بِأَن تَأْتُوا۟ ٱلْبُيُوتَ مِن ظُهُورِهَا وَلَـَٰكِنَّ ٱلْبِرَّ
مَنِ ٱتَّقَىٰ ۗ وَأْتُوا۟ ٱلْبُيُوتَ مِنْ أَبْوَٰبِهَا ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ
لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿١٨٩﴾ وَقَـٰتِلُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ٱلَّذِينَ
يُقَـٰتِلُونَكُمْ وَلَا تَعْتَدُوٓا۟ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلْمُعْتَدِينَ ﴿١٩٠﴾

(187) An halatta muku saduwa da matanku a daren azumi. Su sutura ne a gare ku, ku ma kuma sutura ne a gare su. Allah Ya san cewa ku lalle kun kasance kuna ha'intar kawunanku, sai Ya karɓi tubanku kuma Ya yi muku afuwa; to a yanzu ku sadu da su (da daddare), kuma ku nemi abin da Allah Ya rubuta muku, kuma ku ci, kuma ku sha har farin zare ya bayyana a gare ku daga baƙin zare na alfijir (wato ketowar Alfijir), sannan kuma ku cika azumi zuwa dare, kuma kar ku sadu da su alhali kuna i'itikafia masallatai. Waɗannan iyakoki ne na Allah, kada ku kusance su. Kamar haka ne Allah Yake bayyana ayoyinsa ga mutane, don su samu taƙawa

(188) Kuma kada ku ci dukiyoyinku a tsakaninku ta hanyar rashin gaskiya, haka kuma kada ku miƙa dukiyoyinku zuwa ga masu shari'a, don kawai ku ci wani ɓangare na dukiyar mutane ta hanyar saɓo, alhali kuna sane

(189) Suna tambayar ka dangane da jirajiran wata. Ka ce: "Su lokuta ne (don amfani) ga mutane da (tantance lokacin) Hajji." Kuma ba ya daga cikin aikin ɗa'a, ku zo wa gidaje ta bayansu, sai dai mai aikin ɗa'a shi ne wanda ya yi taƙawa. Kuma ku shigo wa gidajen ta ƙofofinsu, kuma ku kiyaye dokokin Allah don ku rabauta

(190) Kuma ku yaƙi waɗanda suke yaƙar ku don ku ɗaukaka kalmar Allah, kuma kada ku ƙetare iyaka. Lalle Allah ba Ya son masu ƙetare iyaka

وَٱقْتُلُوهُمْ حَيْثُ ثَقِفْتُمُوهُمْ وَأَخْرِجُوهُم مِّنْ حَيْثُ أَخْرَجُوكُمْ ۚ وَٱلْفِتْنَةُ
أَشَدُّ مِنَ ٱلْقَتْلِ ۚ وَلَا تُقَٰتِلُوهُمْ عِندَ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ حَتَّىٰ يُقَٰتِلُوكُمْ
فِيهِ ۖ فَإِن قَٰتَلُوكُمْ فَٱقْتُلُوهُمْ ۗ كَذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿١٩١﴾ فَإِنِ ٱنتَهَوْا۟
فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٩٢﴾ وَقَٰتِلُوهُمْ حَتَّىٰ لَا تَكُونَ فِتْنَةٌ وَيَكُونَ
ٱلدِّينُ لِلَّهِ ۖ فَإِنِ ٱنتَهَوْا۟ فَلَا عُدْوَٰنَ إِلَّا عَلَى ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٩٣﴾ ٱلشَّهْرُ ٱلْحَرَامُ
بِٱلشَّهْرِ ٱلْحَرَامِ وَٱلْحُرُمَٰتُ قِصَاصٌ ۚ فَمَنِ ٱعْتَدَىٰ عَلَيْكُمْ فَٱعْتَدُوا۟
عَلَيْهِ بِمِثْلِ مَا ٱعْتَدَىٰ عَلَيْكُمْ ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ مَعَ
ٱلْمُتَّقِينَ ﴿١٩٤﴾ وَأَنفِقُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَا تُلْقُوا۟ بِأَيْدِيكُمْ إِلَى ٱلتَّهْلُكَةِ ۚ
وَأَحْسِنُوٓا۟ ۛ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿١٩٥﴾ وَأَتِمُّوا۟ ٱلْحَجَّ وَٱلْعُمْرَةَ لِلَّهِ ۚ
فَإِنْ أُحْصِرْتُمْ فَمَا ٱسْتَيْسَرَ مِنَ ٱلْهَدْىِ ۖ وَلَا تَحْلِقُوا۟ رُءُوسَكُمْ حَتَّىٰ يَبْلُغَ
ٱلْهَدْىُ مَحِلَّهُۥ ۚ فَمَن كَانَ مِنكُم مَّرِيضًا أَوْ بِهِۦٓ أَذًى مِّن رَّأْسِهِۦ فَفِدْيَةٌ
مِّن صِيَامٍ أَوْ صَدَقَةٍ أَوْ نُسُكٍ ۚ فَإِذَآ أَمِنتُمْ فَمَن تَمَتَّعَ بِٱلْعُمْرَةِ إِلَى ٱلْحَجِّ
فَمَا ٱسْتَيْسَرَ مِنَ ٱلْهَدْىِ ۚ فَمَن لَّمْ يَجِدْ فَصِيَامُ ثَلَٰثَةِ أَيَّامٍ فِى ٱلْحَجِّ
وَسَبْعَةٍ إِذَا رَجَعْتُمْ ۗ تِلْكَ عَشَرَةٌ كَامِلَةٌ ۗ ذَٰلِكَ لِمَن لَّمْ يَكُنْ أَهْلُهُۥ حَاضِرِى
ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿١٩٦﴾

(191) Kuma ku yaƙe su duk inda kuka same su, kuma ku fitar da su ta inda suka fitar da ku; kuma fitina (ta kafirci) ita ce mafi tsanani fiye da kisa, kuma kada ku yaƙe su a wurin Masallaci mai alfarma, har sai idan sun yaƙe ku a cikinsa, idan har suka yaƙe ku, to ku ma ku yaƙe su. Kamar haka ne sakamakon kafirai yake

(192) Amma idan suka daina, to lalle Allah Mai yawan gafara ne, Mai jin ƙai

(193) Kuma ku yaƙe su har ya zamanto babu wata fitina, kuma addini ya zamo na Allah ne. Idan suka daina, to babu sauran kai farmaki sai a kan azzalumai

(194) (Idan sun yaƙe ku a) wata mai alfarma[1], (ku ma ku yaƙe su a) wata mai alfarma, kuma a cikin abubuwa masu alfarma akwai ƙisasi. Don haka duk wanda ya yi muku ta'addanci, to ku ma ku rama ta'addancin gwargwadon yadda ya yi muku ta'addanci; kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku sani lalle Allah Yana tare da masu taƙawa

(195) Kuma ku ciyar da dukiyoyinku a hanyar Allah, kuma kada ku jefa kawunanku zuwa ga halaka, kuma ku kyautata; lalle Allah Yana son masu kyautatawa

(196) Kuma ku cika aikin Hajji da umara domin Allah. To idan an tsare ku, sai ku gabatar da abin da ya sawwaƙa na hadaya, kuma kada ku aske kawunanku har sai hadaya ta kai wurin yankanta. To wanda ya kasance a cikinku mara lafiya ko akwai wata cuta a kansa, (idan yayi aski) to sai ya yi fidiya ta (hanyar) yin azumi ko sadaƙa ko yanka[2]. Idan kuwa kun amintu, to duk wanda ya yi tamattu'i da yin umara tare da Hajji, to sai ya yanka abin da ya sawwaƙa na hadaya; amma wanda bai samu ba, sai ya yi azumin kwana uku a lokacin aikin Hajji, da kuma na kwana bakwai idan kun dawo gida. Waɗannan kwana goma ke nan cikakku. Wannan hukuncin yana ga wanda iyalinsa ba sa cikin hurumin Makka ne. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, ku sani cewa, lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne

(1) Watanni masu alfarma huɗu ne, su ne: Zulƙi'ida, Zulhijja, Al-Muharram da Rajab.

(2) Watau ya yi azumi na kwana uku, ko ya ciyar da miskinai shida, kowanne ya ba shi rabin mudu ko ya yanka akuya.

الْحَجُّ أَشْهُرٌ مَّعْلُومَاتٌ ۚ فَمَن فَرَضَ فِيهِنَّ الْحَجَّ فَلَا
رَفَثَ وَلَا فُسُوقَ وَلَا جِدَالَ فِي الْحَجِّ ۗ وَمَا تَفْعَلُوا مِنْ
خَيْرٍ يَعْلَمْهُ اللَّهُ ۗ وَتَزَوَّدُوا فَإِنَّ خَيْرَ الزَّادِ التَّقْوَىٰ ۚ
وَاتَّقُونِ يَا أُولِي الْأَلْبَابِ ﴿١٩٧﴾ لَيْسَ عَلَيْكُمْ جُنَاحٌ
أَن تَبْتَغُوا فَضْلًا مِّن رَّبِّكُمْ ۚ فَإِذَا أَفَضْتُم مِّنْ
عَرَفَاتٍ فَاذْكُرُوا اللَّهَ عِندَ الْمَشْعَرِ الْحَرَامِ ۖ
وَاذْكُرُوهُ كَمَا هَدَاكُمْ وَإِن كُنتُم مِّن قَبْلِهِ
لَمِنَ الضَّالِّينَ ﴿١٩٨﴾ ثُمَّ أَفِيضُوا مِنْ حَيْثُ أَفَاضَ
النَّاسُ وَاسْتَغْفِرُوا اللَّهَ ۚ إِنَّ اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٩٩﴾
فَإِذَا قَضَيْتُم مَّنَاسِكَكُمْ فَاذْكُرُوا اللَّهَ كَذِكْرِكُمْ
آبَاءَكُمْ أَوْ أَشَدَّ ذِكْرًا ۗ فَمِنَ النَّاسِ مَن يَقُولُ
رَبَّنَا آتِنَا فِي الدُّنْيَا وَمَا لَهُ فِي الْآخِرَةِ مِنْ خَلَاقٍ
﴿٢٠٠﴾ وَمِنْهُم مَّن يَقُولُ رَبَّنَا آتِنَا فِي الدُّنْيَا حَسَنَةً
وَفِي الْآخِرَةِ حَسَنَةً وَقِنَا عَذَابَ النَّارِ ﴿٢٠١﴾ أُولَٰئِكَ
لَهُمْ نَصِيبٌ مِّمَّا كَسَبُوا ۚ وَاللَّهُ سَرِيعُ الْحِسَابِ ﴿٢٠٢﴾

(197) (Lokacin) hajji wasu watanni ne sanannu[1]. Don haka duk wanda ya wajabta wa kansa aikin Hajji cikin waɗannan (watanni), to babu maganar saduwa da mace, kuma babu fasiƙanci, kuma babu jayayya a cikin aikin Hajji. Kuma duk abin da kuka aikata na alheri, Allah Yana sane da shi. Kuma ku yi guzuri, amma mafificin guzuri shi ne taƙawa, kuma ku kiyaye dokokina ya ku ma'abota hankula

(198) Babu wani laifi gare ku ku nemi falala daga Ubangijinku, don haka idan kun gangaro daga Arfa, to ku ambaci Allah a wurin (da ake kira) Mash'arul Haraam, kuma ku ambace Shi kamar yadda Ya shiryar da ku, ko da yake a da tabbas kun kasance daga cikin ɓatattu


(199) Sannan kuma sai ku gangaro ta inda mutane suka gangaro kuma ku nemi gafarar Allah; lalle Allah Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai

(200) To idan kun gama ayyukanku na Hajji, to ku yi ta ambaton Allah kamar yadda kuke ambaton iyayenku, ko ambaton (Allah) ya fi yawa. To daga cikin mutane akwai wanda yake cewa: "Ya Ubangijimu, Ka ba mu (rabo) a nan duniya", kuma a lahira ba shi da wani rabo

(201) Kuma daga cikinsu akwai wanda yake cewa: "Ya Ubangijinmu, Ka ba mu kyakkyawa a nan duniya, kuma Ka ba mu kyakkyawa a lahira, Ka kuma tsare mu daga azabar wuta."

(202) Waɗannan suna da babban rabo na daga abin da suka aikata, kuma Allah Mai gaggawar hisabi ne

(1) Su ne: Shawwal da Zulƙi'ida da Zulhijja.


* وَٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ فِيٓ أَيَّامٖ مَّعۡدُودَٰتٖۚ فَمَن تَعَجَّلَ فِي
يَوۡمَيۡنِ فَلَآ إِثۡمَ عَلَيۡهِۖ وَمَن تَأَخَّرَ فَلَآ إِثۡمَ عَلَيۡهِۚ لِمَنِ
ٱتَّقَىٰۗ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّكُمۡ إِلَيۡهِ تُحۡشَرُونَ
٢٠٣ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يُعۡجِبُكَ قَوۡلُهُۥ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا
وَيُشۡهِدُ ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا فِي قَلۡبِهِۦ وَهُوَ أَلَدُّ ٱلۡخِصَامِ ٢٠٤
وَإِذَا تَوَلَّىٰ سَعَىٰ فِي ٱلۡأَرۡضِ لِيُفۡسِدَ فِيهَا وَيُهۡلِكَ ٱلۡحَرۡثَ
وَٱلنَّسۡلَۚ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلۡفَسَادَ ٢٠٥ وَإِذَا قِيلَ لَهُ ٱتَّقِ ٱللَّهَ
أَخَذَتۡهُ ٱلۡعِزَّةُ بِٱلۡإِثۡمِۚ فَحَسۡبُهُۥ جَهَنَّمُۚ وَلَبِئۡسَ
ٱلۡمِهَادُ ٢٠٦ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَشۡرِي نَفۡسَهُ ٱبۡتِغَآءَ
مَرۡضَاتِ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ رَءُوفُۢ بِٱلۡعِبَادِ ٢٠٧ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ ٱدۡخُلُواْ فِي ٱلسِّلۡمِ كَآفَّةٗ وَلَا تَتَّبِعُواْ خُطُوَٰتِ
ٱلشَّيۡطَٰنِۚ إِنَّهُۥ لَكُمۡ عَدُوّٞ مُّبِينٞ ٢٠٨ فَإِن زَلَلۡتُم مِّنۢ بَعۡدِ
مَا جَآءَتۡكُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُ فَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٞ
٢٠٩ هَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّآ أَن يَأۡتِيَهُمُ ٱللَّهُ فِي ظُلَلٖ مِّنَ ٱلۡغَمَامِ
وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَقُضِيَ ٱلۡأَمۡرُۚ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرۡجَعُ ٱلۡأُمُورُ ٢١٠

(203) Kuma ku ambaci Allah a cikin wasu kwanaki ƙididdigaggu. To duk wanda ya yi gaggawar (barin Mina) cikin kwana biyu, to babu laifi a gare shi; wanda kuwa ya yi jinkiri, to babu laifi a gare shi, (amma dukkansu) ga wanda ya yi taƙawa. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku sani cewa, zuwa gare Shi za a tattara ku

(204) Kuma daga cikin mutane akwai wanda zancensa yake burge ka a rayuwar duniya, kuma yana shaidar da Allah ga abin da yake cikin zuciyarsa, alhali kuwa shi mai tsananin husuma ne

(205) Kuma idan ya juya baya, zai yi ta yawo a cikin ƙasa don ya yi ɓarna a cikinta, kuma ya lalata amfanin gona da dabbobi. Allah kuwa ba Ya son ɓarna

(206) Idan kuma aka ce masa: "Ka kiyaye dokokin Allah" sai girman kai ya kama shi saboda saɓo. To Jahannama ta ishe shi (makwanci), kuma lalle tir da wannan makwanci

(207) Kuma daga cikin mutane akwai wanda yake sayar da kansa don neman yardar Allah. Allah kuwa Mai yawan tausayi ne ga bayi

(208)Ya ku waɗanda suka yi imani, ku shiga cikin addinin Musulunci gaba ɗaya, kuma kar ku bi hanyoyin Shaiɗan. Lalle shi maƙiyi ne a gare ku, mai bayyana (ƙiyayya)

(209) To idan kuka zame bayan hujjoji bayyanannu sun zo muku, to ku sani cewa, lalle Allah Mabuwayi ne, Mai hikima

(210) Shin ko akwai abin da suke jira ne, in ban da Allah Ya zo musu a cikin waɗansu inuwoyi na gizagizai da mala'iku, sai a zartar da al'amari? Kuma zuwa ga Allah ne ake mayar da al'amura

سَلۡ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ كَمۡ ءَاتَيۡنَٰهُم مِّنۡ ءَايَةم بَيِّنَةٖۗ وَمَن يُبَدِّلۡ نِعۡمَةَ
ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَتۡهُ فَإِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ٢١١ زُيِّنَ
لِلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا وَيَسۡخَرُونَ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَٱلَّذِينَ
ٱتَّقَوۡاْ فَوۡقَهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ وَٱللَّهُ يَرۡزُقُ مَن يَشَآءُ بِغَيۡرِ حِسَابٖ
٢١٢ كَانَ ٱلنَّاسُ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ فَبَعَثَ ٱللَّهُ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مُبَشِّرِينَ
وَمُنذِرِينَ وَأَنزَلَ مَعَهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ لِيَحۡكُمَ بَيۡنَ ٱلنَّاسِ
فِيمَا ٱخۡتَلَفُواْ فِيهِۚ وَمَا ٱخۡتَلَفَ فِيهِ إِلَّا ٱلَّذِينَ أُوتُوهُ مِنۢ بَعۡدِ
مَا جَآءَتۡهُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُ بَغۡيَۢا بَيۡنَهُمۡۖ فَهَدَى ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
لِمَا ٱخۡتَلَفُواْ فِيهِ مِنَ ٱلۡحَقِّ بِإِذۡنِهِۦۗ وَٱللَّهُ يَهۡدِي مَن يَشَآءُ
إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٍ ٢١٣ أَمۡ حَسِبۡتُمۡ أَن تَدۡخُلُواْ ٱلۡجَنَّةَ وَلَمَّا
يَأۡتِكُم مَّثَلُ ٱلَّذِينَ خَلَوۡاْ مِن قَبۡلِكُمۖ مَّسَّتۡهُمُ ٱلۡبَأۡسَآءُ وَٱلضَّرَّآءُ
وَزُلۡزِلُواْ حَتَّىٰ يَقُولَ ٱلرَّسُولُ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ مَتَىٰ نَصۡرُ
ٱللَّهِۗ أَلَآ إِنَّ نَصۡرَ ٱللَّهِ قَرِيبٞ ٢١٤ يَسۡـَٔلُونَكَ مَاذَا يُنفِقُونَۖ قُلۡ
مَآ أَنفَقۡتُم مِّنۡ خَيۡرٖ فَلِلۡوَٰلِدَيۡنِ وَٱلۡأَقۡرَبِينَ وَٱلۡيَتَٰمَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينِ
وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِۗ وَمَا تَفۡعَلُواْ مِنۡ خَيۡرٖ فَإِنَّ ٱللَّهَ بِهِۦ عَلِيمٞ ٢١٥

(211) Ka tambayi Banu Isra'ila, sau nawa Muka ba su wata aya bayyananniya? Kuma duk wanda ya musanya ni'imar Allah bayan ta zo masa, to lalle Allah Mai tsananin ukuba ne

(212) An ƙawata wa kafirai rayuwar duniya, kuma suna yin izgili ga waɗanda suka yi imani. Waɗanda kuwa suka yi taƙawa su ne a samansu a ranar alƙiyama. Kuma Allah Yana arzurta wanda ya ga dama, ba tare da lissafi ba

(213) Mutane sun kasance al'umma guda ɗaya, sai Allah Ya aiko da annabawa, suna masu albishir, kuma masu gargaɗi, kuma Ya saukar da littafi tare da su da gaskiya, don ya yi hukunci tsakanin mutane cikin abin da suka yi saɓani a kansa. Kuma ba wasu ne suka yi saɓani a kansa ba sai waɗanda aka ba wa shi, bayan hujjoji bayyanannu sun zo musu, don zalunci a tsakaninsu; sai Allah Ya shiryar da waɗanda suka yi imani ga abin da (mutane) suka yi saɓani cikinsa na gaskiya da izininsa. Kuma Allah Yana shiryar da wanda Ya ga dama zuwa ga tafarki madaidaici

(214) Shin kun yi tsammanin za ku shiga Aljanna ne, alhalin misalin irin abin da ya shafi waɗanda suka shuɗe gabaninku bai zo muku ba? Tsananin talauci da cuta sun shafe su; kuma an girgiza su sosai, har Manzo da waɗanda suka yi imani tare da shi suka ƙi cewa: "Yaushe ne nasarar Allah za ta zo?" Ku saurara, lalle nasarar Allah a kusa take

(215) Suna tambayar ka, me za su ciyar ne? Ka ce: "Duk abin da za ku ciyar na alheri, to ga mahaifa da dangi mafiya kusanci da marayu da miskinai da matafiyi. Kuma duk abin da kuka aikata na alheri, to lalle Allah Masani ne da shi."

كُتِبَ عَلَيْكُمُ ٱلْقِتَالُ وَهُوَ كُرْهٌ لَّكُمْ ۖ وَعَسَىٰٓ أَن تَكْرَهُوا۟
شَيْـًٔا وَهُوَ خَيْرٌ لَّكُمْ ۖ وَعَسَىٰٓ أَن تُحِبُّوا۟ شَيْـًٔا وَهُوَ شَرٌّ
لَّكُمْ ۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿٢١٦﴾ يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلشَّهْرِ
ٱلْحَرَامِ قِتَالٍ فِيهِ ۖ قُلْ قِتَالٌ فِيهِ كَبِيرٌ ۚ وَصَدٌّ عَن سَبِيلِ
ٱللَّهِ وَكُفْرٌۢ بِهِۦ وَٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ وَإِخْرَاجُ أَهْلِهِۦ مِنْهُ
أَكْبَرُ عِندَ ٱللَّهِ ۚ وَٱلْفِتْنَةُ أَكْبَرُ مِنَ ٱلْقَتْلِ ۗ وَلَا يَزَالُونَ
يُقَٰتِلُونَكُمْ حَتَّىٰ يَرُدُّوكُمْ عَن دِينِكُمْ إِنِ ٱسْتَطَٰعُوا۟ ۚ وَمَن
يَرْتَدِدْ مِنكُمْ عَن دِينِهِۦ فَيَمُتْ وَهُوَ كَافِرٌ فَأُو۟لَٰٓئِكَ
حَبِطَتْ أَعْمَٰلُهُمْ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْـَٔاخِرَةِ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ
ٱلنَّارِ ۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿٢١٧﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَٱلَّذِينَ
هَاجَرُوا۟ وَجَٰهَدُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ أُو۟لَٰٓئِكَ يَرْجُونَ رَحْمَتَ
ٱللَّهِ ۚ وَٱللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٢١٨﴾ ۞ يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْخَمْرِ وَٱلْمَيْسِرِ ۖ
قُلْ فِيهِمَآ إِثْمٌ كَبِيرٌ وَمَنَٰفِعُ لِلنَّاسِ وَإِثْمُهُمَآ أَكْبَرُ
مِن نَّفْعِهِمَا ۗ وَيَسْـَٔلُونَكَ مَاذَا يُنفِقُونَ ۖ قُلِ ٱلْعَفْوَ ۗ كَذَٰلِكَ
يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلْـَٔايَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَتَفَكَّرُونَ ﴿٢١٩﴾

(216) An wajabta muku yaƙi (ku muminai), ga shi kuwa kuna ƙin sa, kuma zai iya yiwuwa ku ƙi wani abu alhalin shi alheri ne a gare ku, kuma zai iya yiwuwa ku so wani abu alhalin shi sharri ne a gare ku. Kuma Allah Shi yake da sani, ku ba ku sani ba

(217) Suna tambayar ka game da wata mai alfarma, yin yaƙi a cikinsa. Ka ce: "Yaƙi a cikinsa, babban laifi ne, amma hana (mutane) bin tafarkin Allah da kafirce masa da kuma (hana mutane shiga) Masallaci mai alfarma da fitar da mutanensa daga gare shi, su ne mafi girman laifi a wajen Allah. Kuma (laifin) fitina ya fi na kisa girma."[1] Kuma (kafirai) ba za su gushe ba suna yaƙar ku, har sai sun raba ku da addininku, idan da za su sami dama. Kuma duk wanda ya yi ridda daga cikinku, ya bar addininsa, kuma ya mutu yana kafiri, to waɗannan ayyukansu sun lalace a duniya da lahira, kuma waɗannan su ne ma'abota wuta, suna masu dawwama a cikinta

(218) Lalle waɗanda suka yi imani da kuma waɗanda suka yi hijira, kuma suka yi jihadi don Allah, waɗannan su ne suke fatan rahamar Allah; Allah kuwa Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai

(219) Suna tambayar ka game da giya da caca. Ka ce: "A cikin lamarinsu akwai zunubi mai girma da kuma waɗansu amfanunnuka ga mutane. Amma zunubinsu ya fi amfaninsu girma"[2] Kuma suna tambayar ka, me za su ciyar? Ka ce: "Abin da ya daɗu a kan buƙatunku." Kamar haka ne Allah Yake muku bayanin ayoyi don ku yi tunani

(1) Wannan ayar ta sauka ne bayan da wata runduna ta Musulmi suka kashe wani kafiri mai suna Ibnul Hadhrami a watan Rajab ba su sani ba. Sai kafirai suka riƙa aibata su da haka, sai Allah ya saukar da wannan ayar.

(2) Wannan matakin farko ne na tsawatarwa game da giya. Allah ya haramta giya gaba ɗaya a Suratul Ma'ida, aya ta 90-91

فِي ٱلدُّنْيَا وَٱلْـَٔاخِرَةِ ۗ وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْيَتَٰمَىٰ ۖ قُلْ إِصْلَاحٌ لَّهُمْ
خَيْرٌ ۖ وَإِن تُخَالِطُوهُمْ فَإِخْوَٰنُكُمْ ۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ ٱلْمُفْسِدَ مِنَ
ٱلْمُصْلِحِ ۚ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ لَأَعْنَتَكُمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ
﴿٢٢٠﴾ وَلَا تَنكِحُوا۟ ٱلْمُشْرِكَٰتِ حَتَّىٰ يُؤْمِنَّ ۚ وَلَأَمَةٌ مُّؤْمِنَةٌ
خَيْرٌ مِّن مُّشْرِكَةٍ وَلَوْ أَعْجَبَتْكُمْ ۗ وَلَا تُنكِحُوا۟ ٱلْمُشْرِكِينَ
حَتَّىٰ يُؤْمِنُوا۟ ۚ وَلَعَبْدٌ مُّؤْمِنٌ خَيْرٌ مِّن مُّشْرِكٍ وَلَوْ أَعْجَبَكُمْ ۗ
أُو۟لَٰٓئِكَ يَدْعُونَ إِلَى ٱلنَّارِ ۖ وَٱللَّهُ يَدْعُوٓا۟ إِلَى ٱلْجَنَّةِ وَٱلْمَغْفِرَةِ
بِإِذْنِهِۦ ۖ وَيُبَيِّنُ ءَايَٰتِهِۦ لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿٢٢١﴾
وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْمَحِيضِ ۖ قُلْ هُوَ أَذًى فَٱعْتَزِلُوا۟ ٱلنِّسَآءَ فِى
ٱلْمَحِيضِ وَلَا تَقْرَبُوهُنَّ حَتَّىٰ يَطْهُرْنَ ۖ فَإِذَا تَطَهَّرْنَ فَأْتُوهُنَّ
مِنْ حَيْثُ أَمَرَكُمُ ٱللَّهُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلتَّوَّٰبِينَ وَيُحِبُّ ٱلْمُتَطَهِّرِينَ
﴿٢٢٢﴾ نِسَآؤُكُمْ حَرْثٌ لَّكُمْ فَأْتُوا۟ حَرْثَكُمْ أَنَّىٰ شِئْتُمْ ۖ وَقَدِّمُوا۟
لِأَنفُسِكُمْ ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّكُم مُّلَٰقُوهُ ۗ وَبَشِّرِ
ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٢٢٣﴾ وَلَا تَجْعَلُوا۟ ٱللَّهَ عُرْضَةً لِّأَيْمَٰنِكُمْ أَن تَبَرُّوا۟
وَتَتَّقُوا۟ وَتُصْلِحُوا۟ بَيْنَ ٱلنَّاسِ ۚ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٢٢٤﴾

(220) Game da lamarin duniya da lahira. Kuma suna tambayar ka game da marayu. Ka ce : “Inganta musu dukiyarsu shi ne mafi alheri, kuma in kuka haɗa cimakarku da tasu, to ai ‘yan’uwanku ne. Amma fa Allah Ya san mai son yin ɓarna daga wanda yake son yin gyara. Kuma da Allah Ya ga dama da Ya ƙuntata muku. Lalle Allah Mabuwayi ne, Mai hikima.”

(221) Kuma kada ku auri mata mushirikai har sai sun yi imani, kuma lalle baiwa mumina ta fi ‘ya mushirika alheri, ko da (mushirikar) ta burge ku. Kuma kada ku aurar wa mushirikai har sai sun yi imani; kuma lalle bawa mumini ya fi (ɗa) mushiriki alheri, ko da ya burge ku. Su waɗancan (kafirai), suna kira ne zuwa ga wuta, Allah kuwa Yana kira ne zuwa ga Aljanna da gafara da izininsa, kuma Yana bayyana ayoyinsa ga mutane don su wa’azantu

(222) Kuma suna tambayar ka game da jinin haila. Ka ce: “Shi cuta ne, don haka ku ƙaurace wa mata a (kwanakin) haila, kuma kada ku kusance su har sai sun tsarkaka. To idan suka yi tsarki, sai ku zo musu ta inda Allah Ya umarce ku. Lalle Allah Yana son masu yawan tuba, kuma Yana son masu tsarki.”

(223) Matanku gonaki ne a gare ku, don haka ku zaike wa gonakinku ta inda kuka ga dama, kuma ku gabatar wa kawunanku (laduban da shari’a ta tanadar muku). Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku sani cewa, lalle ku masu saduwa ne da Shi. Kuma ka yi albishir ga muminai

(224) Kuma kada ku mayar da Allah Ya zamanto kariya ga rantse-rantsenku don su hana ku aiki na ɗa’a ko na taƙawa ko na sulhu tsakanin mutane. Kuma Allah Mai ji ne, Masani

لَّا يُؤَاخِذُكُمُ ٱللَّهُ بِٱللَّغۡوِ فِيٓ أَيۡمَٰنِكُمۡ وَلَٰكِن يُؤَاخِذُكُم بِمَا كَسَبَتۡ
قُلُوبُكُمۡۗ وَٱللَّهُ غَفُورٌ حَلِيمٞ ٢٢٥ لِّلَّذِينَ يُؤۡلُونَ مِن نِّسَآئِهِمۡ تَرَبُّصُ
أَرۡبَعَةِ أَشۡهُرٖۖ فَإِن فَآءُو فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٢٢٦ وَإِنۡ عَزَمُواْ
ٱلطَّلَٰقَ فَإِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ٢٢٧ وَٱلۡمُطَلَّقَٰتُ يَتَرَبَّصۡنَ بِأَنفُسِهِنَّ
ثَلَٰثَةَ قُرُوٓءٖۚ وَلَا يَحِلُّ لَهُنَّ أَن يَكۡتُمۡنَ مَا خَلَقَ ٱللَّهُ فِيٓ أَرۡحَامِهِنَّ
إِن كُنَّ يُؤۡمِنَّ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۚ وَبُعُولَتُهُنَّ أَحَقُّ بِرَدِّهِنَّ فِي
ذَٰلِكَ إِنۡ أَرَادُوٓاْ إِصۡلَٰحٗاۚ وَلَهُنَّ مِثۡلُ ٱلَّذِي عَلَيۡهِنَّ بِٱلۡمَعۡرُوفِۚ
وَلِلرِّجَالِ عَلَيۡهِنَّ دَرَجَةٞۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ٢٢٨ ٱلطَّلَٰقُ مَرَّتَانِۖ
فَإِمۡسَاكُۢ بِمَعۡرُوفٍ أَوۡ تَسۡرِيحُۢ بِإِحۡسَٰنٖۗ وَلَا يَحِلُّ لَكُمۡ أَن تَأۡخُذُواْ
مِمَّآ ءَاتَيۡتُمُوهُنَّ شَيۡـٔٗا إِلَّآ أَن يَخَافَآ أَلَّا يُقِيمَا حُدُودَ ٱللَّهِۖ
فَإِنۡ خِفۡتُمۡ أَلَّا يُقِيمَا حُدُودَ ٱللَّهِ فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡهِمَا فِيمَا ٱفۡتَدَتۡ
بِهِۦۗ تِلۡكَ حُدُودُ ٱللَّهِ فَلَا تَعۡتَدُوهَاۚ وَمَن يَتَعَدَّ حُدُودَ ٱللَّهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ
هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٢٢٩ فَإِن طَلَّقَهَا فَلَا تَحِلُّ لَهُۥ مِنۢ بَعۡدُ حَتَّىٰ تَنكِحَ زَوۡجًا
غَيۡرَهُۥۗ فَإِن طَلَّقَهَا فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡهِمَآ أَن يَتَرَاجَعَآ إِن ظَنَّآ أَن
يُقِيمَا حُدُودَ ٱللَّهِۗ وَتِلۡكَ حُدُودُ ٱللَّهِ يُبَيِّنُهَا لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ٢٣٠

(225) Allah ba zai kama ku da yasasshen zance a cikin rantse-rantsenku ba, sai dai zai kama ku da abin da zukatanku suka ƙudurce. Kuma Allah Mai yawan gafara ne, Mai yawan haƙuri (226) Waɗanda suke rantsuwar ba za su sadu da matansu ba, za a yi musu jinkiri na wata huɗu; to idan sun dawo, to lalle Allah Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai (227) Idan kuwa suka yi niyyar saki (a cikin zukatansu), to lalle Allah Mai ji ne, kuma Masani

(228) Kuma mata waɗanda aka saki za su dakatar da kawunansu (tsawon) ƙur'i[1] uku, kuma ba ya halatta a gare su su ɓoye abin da Allah Ya halitta a cikin mahaifarsu, in sun kasance suna yin imani da Allah da ranar ƙarshe; kuma mazajensu su suka fi cancantar dawo da su a cikin wancan lokaci in sun yi nufin sulhu[2]; kuma su (mata) suna da haƙƙi kwatankwacin irin wanda yake kansu ta hanyar da aka sani, kuma mazaje suna da fifiko a kansu. Allah Kuma Mabuwayi ne, Mai hikima (229) Saki sau biyu ne (ɗaya bayan ɗaya), don haka ko dai ya riƙe ta ta hanyar da aka sani, ko kuma ya sake ta tare da kyautatawa. Kuma bai halatta gare ku ba ku karɓi wani abu daga cikin abin da kuka ba su, sai fa idan su (ma'aurata) biyu sun ji tsoron ba za su tsayar da dokokin Allah ba. To idan kuka ji tsoron ba za su tsayar da dokokin Allah ba, to babu laifi a gare su game da abin da ta fanshi kanta da shi[3]. Waɗannan iyakokin Allah ne, kada ku ƙetare su, kuma duk wanda ya ƙetare iyakokin Allah, to waɗannan su ne azzalumai (230) To idan ya sake sakin ta, ba za ta halatta a gare shi ba bayan haka har sai ta auri wani mijin daban[4]. To idan ya sake ta, to babu laifi gare su su koma, idan sun yi zaton cewa za su tsayar da dokokin Allah. Waɗannan dokokin Allah ne, Yake bayyana su ga mutanen da suke da sani

(1) lKur'i a Larabci yana nufin 'haila' ko 'tsarki', A ra'ayin manyan sahabbai, har da Halifofi huɗu da wasu tabi'ai, sun ce, ana nufin 'jinin haila'. Watau iddar wadda aka saki tana ƙare wa da ɗaukewar jinin al'adar ta ta uku bayan sakin.

(2) Mijin da ya saki matarsa saki na farko, ko na biyu, zai iya dawo da ita matuƙar suna son su ci gaba da zama da juna cikin mutuntawa da kyautatawa.

(3) Idan mace ta ga ba za ta iya zama da mijinta ba, to babu laifi ta mayar masa abin da ya kashe, sai su rabu. Wannan shi ne: Khul'u.

(4) Watau aure sahihi, kuma mijin ya tare da ita. Idan daga baya ya sake ta ta kammala iddarta, to za ta iya koma wa wajen mijinta na farko, amma bayan an sake ɗaura musu aure.

وَإِذَا طَلَّقْتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَبَلَغْنَ أَجَلَهُنَّ فَأَمْسِكُوهُنَّ بِمَعْرُوفٍ
أَوْ سَرِّحُوهُنَّ بِمَعْرُوفٍ ۚ وَلَا تُمْسِكُوهُنَّ ضِرَارًا لِّتَعْتَدُوا۟ ۚ وَمَن
يَفْعَلْ ذَٰلِكَ فَقَدْ ظَلَمَ نَفْسَهُۥ ۚ وَلَا تَتَّخِذُوٓا۟ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ هُزُوًا ۚ
وَٱذْكُرُوا۟ نِعْمَتَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَمَآ أَنزَلَ عَلَيْكُم مِّنَ ٱلْكِتَٰبِ وَٱلْحِكْمَةِ
يَعِظُكُم بِهِۦ ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿٢٣١﴾ وَإِذَا
طَلَّقْتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَبَلَغْنَ أَجَلَهُنَّ فَلَا تَعْضُلُوهُنَّ أَن يَنكِحْنَ
أَزْوَٰجَهُنَّ إِذَا تَرَٰضَوْا۟ بَيْنَهُم بِٱلْمَعْرُوفِ ۗ ذَٰلِكَ يُوعَظُ بِهِۦ مَن كَانَ
مِنكُمْ يُؤْمِنُ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ ۗ ذَٰلِكُمْ أَزْكَىٰ لَكُمْ وَأَطْهَرُ ۚ وَٱللَّهُ
يَعْلَمُ وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿٢٣٢﴾ * وَٱلْوَٰلِدَٰتُ يُرْضِعْنَ أَوْلَٰدَهُنَّ حَوْلَيْنِ
كَامِلَيْنِ ۖ لِمَنْ أَرَادَ أَن يُتِمَّ ٱلرَّضَاعَةَ ۚ وَعَلَى ٱلْمَوْلُودِ لَهُۥ رِزْقُهُنَّ
وَكِسْوَتُهُنَّ بِٱلْمَعْرُوفِ ۚ لَا تُكَلَّفُ نَفْسٌ إِلَّا وُسْعَهَا ۚ لَا تُضَآرَّ
وَٰلِدَةٌۢ بِوَلَدِهَا وَلَا مَوْلُودٌ لَّهُۥ بِوَلَدِهِۦ ۚ وَعَلَى ٱلْوَارِثِ مِثْلُ ذَٰلِكَ ۗ فَإِنْ
أَرَادَا فِصَالًا عَن تَرَاضٍ مِّنْهُمَا وَتَشَاوُرٍ فَلَا جُنَاحَ عَلَيْهِمَا ۗ وَإِنْ
أَرَدتُّمْ أَن تَسْتَرْضِعُوٓا۟ أَوْلَٰدَكُمْ فَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ إِذَا سَلَّمْتُم مَّآ
ءَاتَيْتُم بِٱلْمَعْرُوفِ ۗ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿٢٣٣﴾

(231) Kuma idan kuka saki mata, sai wa'adin iddarsu ya kusa, (idan kuna son su) sai ku rike su ta hanyar da ta dace (a shari'ance) ko kuma ku kyale su ta hanyar da ta dace (a shari'ance); kuma kada ku rike su da nufin cutarwa don ku ketare iyakar (Ubangiji). Duk wanda ya aikata haka kuwa, to hakika ya zalunci kansa. Kuma kada ku mayar da ayoyin Allah abin izgili, kuma ku tuna ni'imar Allah da Ya yi muku da abin da Ya saukar muku na Littafi da Hikima Yana yi muku wa'azi da shi. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku sani lalle Allah Masanin komai ne

(232) Kuma idan kun saki mata sai suka cika wa'adin iddarsu, to (ku waliyyai) kada ku hana su su auri mazajensu (na da) idan sun yi yarjejeniya a tsakaninsu ta hanyar da ta dace (a shari'a). Wannan (abin da aka ambata) shi ne wanda ake yin wa'azi da shi ga wanda ya kasance daga cikinku, yana imani da Allah da ranar lahira. Wannan shi ne abin da ya fi alheri a gare ku kuma ya fi tsarki; kuma Allah Shi ne Yake da sani, ku ba ku sani ba

(233) Kuma iyaye mata za su shayar da 'ya'yansu tsawon shekara biyu cikakku, ga wanda ya yi nufin ya cika wa'adi na shayarwa. Kuma wajibi ne a kan wanda aka yi wa haihuwa ya ciyar da su (mata masu shayarwa) da yi musu tufafi ta hanyar da aka saba. Ba a ɗora wa wani rai sai abin da zai iya. Kar a cutar da uwa saboda ɗanta, haka kuma kar a cutar da uba saboda ɗansa. Kuma kwatankwacin irin wannan ya wajaba kan magajinsa. To idan su biyun sun yi nufin yaye bisa ga yarjejeniya da shawara da junansu, to babu laifi a kansu. Kuma idan kun yi nufin nema wa 'ya'yanku mai shayarwa, to babu laifi a kanku idan kun bayar da abin da ya kamata ta yadda aka saba. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku sani cewa, lalle Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne

وَٱلَّذِينَ يُتَوَفَّوْنَ مِنكُمْ وَيَذَرُونَ أَزْوَٰجًا يَتَرَبَّصْنَ بِأَنفُسِهِنَّ
أَرْبَعَةَ أَشْهُرٍ وَعَشْرًا ۖ فَإِذَا بَلَغْنَ أَجَلَهُنَّ فَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ
فِيمَا فَعَلْنَ فِىٓ أَنفُسِهِنَّ بِٱلْمَعْرُوفِ ۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ
﴿٢٣٤﴾ وَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ فِيمَا عَرَّضْتُم بِهِۦ مِنْ خِطْبَةِ ٱلنِّسَآءِ
أَوْ أَكْنَنتُمْ فِىٓ أَنفُسِكُمْ ۚ عَلِمَ ٱللَّهُ أَنَّكُمْ سَتَذْكُرُونَهُنَّ
وَلَٰكِن لَّا تُوَاعِدُوهُنَّ سِرًّا إِلَّآ أَن تَقُولُوا۟ قَوْلًا مَّعْرُوفًا ۚ
وَلَا تَعْزِمُوا۟ عُقْدَةَ ٱلنِّكَاحِ حَتَّىٰ يَبْلُغَ ٱلْكِتَٰبُ أَجَلَهُۥ ۚ
وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِىٓ أَنفُسِكُمْ فَٱحْذَرُوهُ ۚ وَٱعْلَمُوٓا۟
أَنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ حَلِيمٌ ﴿٢٣٥﴾ لَّا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ إِن طَلَّقْتُمُ ٱلنِّسَآءَ
مَا لَمْ تَمَسُّوهُنَّ أَوْ تَفْرِضُوا۟ لَهُنَّ فَرِيضَةً ۚ وَمَتِّعُوهُنَّ عَلَى
ٱلْمُوسِعِ قَدَرُهُۥ وَعَلَى ٱلْمُقْتِرِ قَدَرُهُۥ مَتَٰعًۢا بِٱلْمَعْرُوفِ ۖ حَقًّا عَلَى
ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٢٣٦﴾ وَإِن طَلَّقْتُمُوهُنَّ مِن قَبْلِ أَن تَمَسُّوهُنَّ وَقَدْ
فَرَضْتُمْ لَهُنَّ فَرِيضَةً فَنِصْفُ مَا فَرَضْتُمْ إِلَّآ أَن يَعْفُونَ
أَوْ يَعْفُوَا۟ ٱلَّذِى بِيَدِهِۦ عُقْدَةُ ٱلنِّكَاحِ ۚ وَأَن تَعْفُوٓا۟ أَقْرَبُ لِلتَّقْوَىٰ ۚ
وَلَا تَنسَوُا۟ ٱلْفَضْلَ بَيْنَكُمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿٢٣٧﴾

(234) Kuma waɗanda suke mutuwa daga cikinku, suna kuma barin mata na aure, (su matan) za su yi zaman jira na wata huɗu da kwana goma. To idan sun cika wa'adinsu, babu laifi a kanku (waliyyansu) cikin duk abin da suka aikata game da kawunansu ta hanyar da aka saba (a shari'a). Kuma Allah Mai cikakken sani ne game da abin da kuke aikatawa

(235) Kuma babu laifi a kanku game da abin da kuka yi wa mata jirwaye da shi na neman aurensu ko kuma kuka ɓoye a cikin zukatanku, Allah Ya san cewa ku za ku riƙa maganarsu, sai dai kar ku yi alƙawari da su (na aure) a asirce, sai dai in za ku faɗi zance wanda yake sananne a (shari'a). Kuma kada ku ƙulla igiyar aure (da mata masu takaba) har sai faralin idda ya cika wa'adinsa. Kuma ku sani lalle Allah Ya san abin da yake cikin zukatanku, don haka ku kiyaye Shi. Kuma ku sani lalle Allah Mai yawan gafara ne, Mai haƙuri

(236) Babu laifi (sadaƙi) a kanku idan kun saki mata, matuƙar ba ku riga kun sadu da su ko kuma kun yanka musu sadaki sananne ba. Sai ku yi musu kyauta (ta kwantar da hankali); mai yalwa daidai yalwarsa; talaka ma daidai ƙarfinsa. (Wannan) wata kyauta ce (da za a bayar) ta hanyar da aka saba; haƙƙi ne a kan masu kyautatawa[1]

(237) Idan kuwa kun sake su ne tun kafin ku sadu da su, alhalin kuma kun yanka musu sadaki, to sai (ku bayar) da rabin abin da kuka yanka, sai fa in su matan sun yi afuwa ko kuma wanda a hannunsa igiyar aure take ya yi afuwa[2]; kuma ku yi afuwa shi ya fi kusa ga taƙawa. Kuma kada ku manta da kyautatawar da take tsakaninku. Lalle Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne

(1) Allah ya yi umarni ga mijin wanda ya saki matarsa kafin ya tare da ita, lalle ya yi mata wata kyauta ta kwantar da hankali gwargwadon ƙarfinsa.

(2) Wanda igiyar aure take hannusa, shi ne mijin. Yana iya yafe wa, ya bar mata duk sadakin baki ɗaya.

حَٰفِظُواْ عَلَى ٱلصَّلَوَٰتِ وَٱلصَّلَوٰةِ ٱلۡوُسۡطَىٰ وَقُومُواْ لِلَّهِ
قَٰنِتِينَ ٢٣٨ فَإِنۡ خِفۡتُمۡ فَرِجَالًا أَوۡ رُكۡبَانٗاۖ فَإِذَآ أَمِنتُمۡ
فَٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ كَمَا عَلَّمَكُم مَّا لَمۡ تَكُونُواْ تَعۡلَمُونَ
٢٣٩ وَٱلَّذِينَ يُتَوَفَّوۡنَ مِنكُمۡ وَيَذَرُونَ أَزۡوَٰجٗا
وَصِيَّةٗ لِّأَزۡوَٰجِهِم مَّتَٰعًا إِلَى ٱلۡحَوۡلِ غَيۡرَ إِخۡرَاجٖۚ فَإِنۡ
خَرَجۡنَ فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡكُمۡ فِي مَا فَعَلۡنَ فِيٓ أَنفُسِهِنَّ
مِن مَّعۡرُوفٖۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ٢٤٠ وَلِلۡمُطَلَّقَٰتِ مَتَٰعُۢ
بِٱلۡمَعۡرُوفِۖ حَقًّا عَلَى ٱلۡمُتَّقِينَ ٢٤١ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ
ٱللَّهُ لَكُمۡ ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تَعۡقِلُونَ ٢٤٢ ۞ أَلَمۡ تَرَ
إِلَى ٱلَّذِينَ خَرَجُواْ مِن دِيَٰرِهِمۡ وَهُمۡ أُلُوفٞ حَذَرَ ٱلۡمَوۡتِ
فَقَالَ لَهُمُ ٱللَّهُ مُوتُواْ ثُمَّ أَحۡيَٰهُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضۡلٍ
عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَشۡكُرُونَ ٢٤٣
وَقَٰتِلُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ٢٤٤ مَّن
ذَا ٱلَّذِي يُقۡرِضُ ٱللَّهَ قَرۡضًا حَسَنٗا فَيُضَٰعِفَهُۥ لَهُۥٓ أَضۡعَافٗا
كَثِيرَةٗۚ وَٱللَّهُ يَقۡبِضُ وَيَبۡصُۜطُ وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٢٤٥

(238) Ku kiyaye salloli da kuma salla mafificiya, kuma ku tsaya domin Allah kuna masu nutsuwa

(239) To idan kuna cikin halin tsoro, sai ku yi salla kuna tafe da ƙafafuwanku ko a kan ababan hawanku. To idan kun amintu, sai ku ambaci Allah kamar yadda Ya sanar da ku abin da ba ku kasance kun sani ba

(240) Kuma waɗanda suke rasuwa daga cikinku suke barin matan aure, (to za su yi) wasiyya ga matansu cewa, a jiyar da su dadi har zuwa shekara, ba tare da an fitar da su ba; to idan su suka fita da kansu, to babu laifi a kanku dangane da abin da suka aikata wa kansu na abin da yake sananne a shari'a. Kuma Allah Mabuwayi ne, Mai hikima[1]

(241) Kuma matan da aka sake su suna da wata kyauta ta kwantar da hankali ta hanyar da aka saba, (wannan) haƙƙi ne a kan masu taƙawa

(242) Kamar haka ne Allah Yake bayyana muku ayoyinsa don ku hankalta

(243) Shin ba ka ga waɗanda suka fita daga gidajensu ba su dubbai don tsoron mutuwa, sai Allah Ya ce da su: "Ku mutu", sannan Ya raya su? Lalle Allah Ma'abocin falala ne ga mutane, sai dai yawancin mutane ba sa godiya

(244) Kuma ku yi yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah, kuma ku sani cewa, lalle Allah Mai ji ne, Masani

(245) Wane ne zai ba wa Allah kyakkyawan rance, sai Ya ninka masa shi ninki mai yawa? Kuma Allah ne Yake kame (dukiya), Yake kuma shimfiɗa ta, kuma zuwa gare Shi za a mayar da ku

(1) Wasu malamai suna ganin wannan aya an shafe ta da aya ta 234. Wasu kuma suna ganin umarni ne ga mazaje su yi wasiyya ga magadansu a kan su ƙale matansu su zauna a gidajensu tsawon shekara ɗaya, Wannan kuwa ya kasance ne kafin Allah ya shar'anta rabon gado, a inda ya ambaci kason mace daga dukiyar mijinta.

أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلْمَلَإِ مِنۢ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ مِنۢ بَعْدِ مُوسَىٰ إِذْ
قَالُوا۟ لِنَبِىٍّ لَّهُمُ ٱبْعَثْ لَنَا مَلِكًا نُّقَٰتِلْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۖ
قَالَ هَلْ عَسَيْتُمْ إِن كُتِبَ عَلَيْكُمُ ٱلْقِتَالُ أَلَّا تُقَٰتِلُوا۟ ۖ
قَالُوا۟ وَمَا لَنَآ أَلَّا نُقَٰتِلَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَقَدْ أُخْرِجْنَا
مِن دِيَٰرِنَا وَأَبْنَآئِنَا ۖ فَلَمَّا كُتِبَ عَلَيْهِمُ ٱلْقِتَالُ تَوَلَّوْا۟
إِلَّا قَلِيلًا مِّنْهُمْ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٢٤٦﴾ وَقَالَ لَهُمْ
نَبِيُّهُمْ إِنَّ ٱللَّهَ قَدْ بَعَثَ لَكُمْ طَالُوتَ مَلِكًا ۚ
قَالُوٓا۟ أَنَّىٰ يَكُونُ لَهُ ٱلْمُلْكُ عَلَيْنَا وَنَحْنُ أَحَقُّ
بِٱلْمُلْكِ مِنْهُ وَلَمْ يُؤْتَ سَعَةً مِّنَ ٱلْمَالِ ۚ قَالَ إِنَّ ٱللَّهَ
ٱصْطَفَىٰهُ عَلَيْكُمْ وَزَادَهُۥ بَسْطَةً فِى ٱلْعِلْمِ وَٱلْجِسْمِ ۖ
وَٱللَّهُ يُؤْتِى مُلْكَهُۥ مَن يَشَآءُ ۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ﴿٢٤٧﴾
وَقَالَ لَهُمْ نَبِيُّهُمْ إِنَّ ءَايَةَ مُلْكِهِۦٓ أَن يَأْتِيَكُمُ
ٱلتَّابُوتُ فِيهِ سَكِينَةٌ مِّن رَّبِّكُمْ وَبَقِيَّةٌ مِّمَّا
تَرَكَ ءَالُ مُوسَىٰ وَءَالُ هَٰرُونَ تَحْمِلُهُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ ۚ
إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً لَّكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٢٤٨﴾

(246) Shin ba ka ga wasu manyan mutane ba daga cikin Banu Isra'ila bayan (mutuwar) Musa yayin da suka faɗa wa Annabinsu: "Ka naɗa mana wani sarki, wanda za mu yi yaƙi (tare da shi) don ɗaukaka kalmar Allah?" Sai ya ce: "Shin ba kwa tsammanin idan an wajabta muku yaƙi, ba za ku yi yaƙin ba?" Sai suka ce: "Me zai sa ba za mu yi yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah ba, alhali kuwa an fitar da mu daga gidajenmu da 'ya'yanmu?" To yayin da aka wajabta musu yaƙin sai suka juya baya sai 'yan kaɗan daga cikinsu. Kuma Allah Masanin azzalumai ne

(247) Kuma Annabinsu ya ce da su: "Lalle haƙiƙa Allah Ya naɗa Ɗalutu ya zama Sarki gare ku." Sai suka ce: "Ta yaya zai samu sarauta a kanmu, alhalin mun fi shi cancatar sarauta, kuma ba a ba shi yalwar dukiya ba?" Sai ya ce: "Lalle Allah Ya zaɓe shi a kanku, kuma Ya ƙara shi da yalwar ilimi da ta girman jiki, kuma Allah Yana bayar da mulkinsa ga wanda Ya ga dama, kuma Allah Mai yalwa ne, Masani."

(248) Sai Annabinsu ya ce da su: "Lalle alamar (cancantar) mulkinsa ita ce akwatin nan da zai zo muku wanda a cikinsa akwai nutsuwa daga Ubangijinku da kuma sauran abin da iyalin Musa suka bari da iyalin Haruna; mala'iku na ɗauke da shi. Lalle a cikin wannan tabbas akwai aya a gare ku, in kun kasance muminai."

فَلَمَّا فَصَلَ طَالُوتُ بِٱلْجُنُودِ قَالَ إِنَّ ٱللَّهَ مُبْتَلِيكُم
بِنَهَرٍ فَمَن شَرِبَ مِنْهُ فَلَيْسَ مِنِّي وَمَن لَّمْ يَطْعَمْهُ
فَإِنَّهُۥ مِنِّيٓ إِلَّا مَنِ ٱغْتَرَفَ غُرْفَةًۢ بِيَدِهِۦ فَشَرِبُوا۟ مِنْهُ
إِلَّا قَلِيلًا مِّنْهُمْ فَلَمَّا جَاوَزَهُۥ هُوَ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟
مَعَهُۥ قَالُوا۟ لَا طَاقَةَ لَنَا ٱلْيَوْمَ بِجَالُوتَ وَجُنُودِهِۦ
قَالَ ٱلَّذِينَ يَظُنُّونَ أَنَّهُم مُّلَٰقُوا۟ ٱللَّهِ كَم مِّن فِئَةٍ
قَلِيلَةٍ غَلَبَتْ فِئَةً كَثِيرَةًۢ بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۗ وَٱللَّهُ مَعَ
ٱلصَّٰبِرِينَ ﴿٢٤٩﴾ وَلَمَّا بَرَزُوا۟ لِجَالُوتَ وَجُنُودِهِۦ قَالُوا۟
رَبَّنَآ أَفْرِغْ عَلَيْنَا صَبْرًا وَثَبِّتْ أَقْدَامَنَا وَٱنصُرْنَا
عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٥٠﴾ فَهَزَمُوهُم بِإِذْنِ ٱللَّهِ
وَقَتَلَ دَاوُۥدُ جَالُوتَ وَءَاتَىٰهُ ٱللَّهُ ٱلْمُلْكَ
وَٱلْحِكْمَةَ وَعَلَّمَهُۥ مِمَّا يَشَآءُ ۗ وَلَوْلَا دَفْعُ ٱللَّهِ ٱلنَّاسَ
بَعْضَهُم بِبَعْضٍ لَّفَسَدَتِ ٱلْأَرْضُ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ ذُو
فَضْلٍ عَلَى ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٢٥١﴾ تِلْكَ ءَايَٰتُ ٱللَّهِ نَتْلُوهَا
عَلَيْكَ بِٱلْحَقِّ ۚ وَإِنَّكَ لَمِنَ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿٢٥٢﴾

(249) To yayin da Dalutu ya fita (bayan gari) da rundunarsa, sai ya ce: “Lalle Allah zai jarrabe ku da wata ƙorama, to duk wanda ya sha daga gare ta, to ba ya tare da ni, duk wanda kuwa bai sha ba, to wannan yana tare da ni, sai dai wanda ya kamfata sau ɗaya da (tafin) hannunsa.” Gaba ɗayansu sai suka sha daga cikinta sai ‘yan kaɗan daga cikinsu (su ne ba su sha ba). To yayin da ya ƙetare shi, shi da waɗanda suka yi imani tare da shi, sai suka ce: “A yau kam ba mu da iko wajen fuskantar Jalutu da rundunarsa.” Sai waɗanda suke da yaƙinin cewa za su haɗu da Allah suka ce: “Sau da yawa wata runduna ‘yan kaɗan takan yi rinjaye a kan wata runduna mai yawa da izinin Allah. Kuma Allah Yana tare da masu haƙuri.”

(250) Kuma yayin da suka yi fito-na-fito da Jalutu da rundunarsa, sai suka ce: “Ya Ubangijinmu, Ka zubo mana haƙuri na musamman, kuma Ka tabbatar da dugaduganmu, kuma Ka taimake mu a kan mutane kafirai.”

(251) Sai suka murƙushe su da izinin Allah, kuma Dawudu ya kashe Jalutu, sai Allah Ya ba shi mulki da hikima, kuma Ya sanar da shi irin abin da Ya ga dama. Ba don yadda Allah Yake kare wani sashin mutane da wani sashi ba, to lalle da ƙasa ta lalace, sai dai kuma Allah Ma’abocin falala ne ga talikai

(252) Waɗannan ayoyin Allah ne, Muna karanta maka su da gaskiya, kuma lalle kai tabbas kana cikin manzanni



* تِلْكَ ٱلرُّسُلُ فَضَّلْنَا بَعْضَهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ ۘ مِّنْهُم مَّن كَلَّمَ ٱللَّهُ ۖ
وَرَفَعَ بَعْضَهُمْ دَرَجَٰتٍ ۚ وَءَاتَيْنَا عِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ ٱلْبَيِّنَٰتِ
وَأَيَّدْنَٰهُ بِرُوحِ ٱلْقُدُسِ ۗ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا ٱقْتَتَلَ ٱلَّذِينَ مِنۢ
بَعْدِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا جَآءَتْهُمُ ٱلْبَيِّنَٰتُ وَلَٰكِنِ ٱخْتَلَفُوا۟
فَمِنْهُم مَّنْ ءَامَنَ وَمِنْهُم مَّن كَفَرَ ۚ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا ٱقْتَتَلُوا۟
وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَفْعَلُ مَا يُرِيدُ ﴿٢٥٣﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَنفِقُوا۟
مِمَّا رَزَقْنَٰكُم مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِىَ يَوْمٌ لَّا بَيْعٌ فِيهِ وَلَا خُلَّةٌ وَلَا
شَفَٰعَةٌ ۗ وَٱلْكَٰفِرُونَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٢٥٤﴾ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ
ٱلْحَىُّ ٱلْقَيُّومُ ۚ لَا تَأْخُذُهُۥ سِنَةٌ وَلَا نَوْمٌ ۚ لَّهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۗ مَن ذَا ٱلَّذِى يَشْفَعُ عِندَهُۥٓ إِلَّا بِإِذْنِهِۦ ۚ يَعْلَمُ
مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ ۖ وَلَا يُحِيطُونَ بِشَىْءٍ مِّنْ عِلْمِهِۦٓ إِلَّا
بِمَا شَآءَ ۚ وَسِعَ كُرْسِيُّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ ۖ وَلَا يَـُٔودُهُۥ حِفْظُهُمَا ۚ
وَهُوَ ٱلْعَلِىُّ ٱلْعَظِيمُ ﴿٢٥٥﴾ لَآ إِكْرَاهَ فِى ٱلدِّينِ ۖ قَد تَّبَيَّنَ ٱلرُّشْدُ مِنَ
ٱلْغَىِّ ۚ فَمَن يَكْفُرْ بِٱلطَّٰغُوتِ وَيُؤْمِنۢ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱسْتَمْسَكَ
بِٱلْعُرْوَةِ ٱلْوُثْقَىٰ لَا ٱنفِصَامَ لَهَا ۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٢٥٦﴾

(253) Wadannan manzanni, Mun fifita sashinsu a kan sashi. Cikinsu akwai wanda Allah Ya yi magana da shi, kuma Ya ɗaukaka wasunsu da darajoji. Kuma Mun bai wa Isa ɗan Maryam hujjoji bayyanannu, kuma Mun ƙarfafe shi da Ruhi mai tsarki. Da kuma Allah Ya ga dama da wadanda suka zo bayansu ba su yaƙi juna ba bayan hujjoji bayanannu sun zo musu, sai dai kuma sun yi saɓani; cikinsu akwai wanda ya yi imani, kuma cikinsu akwai wanda ya kafirce, kuma da Allah Ya ga dama da ba su yaƙi juna ba, sai dai Allah

Yana aikata abin da Yake nufi

(254) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ciyar daga abin da Muka arzurta ku (da shi) tun kafin wani yini ya zo wanda babu ciniki a cikinsa kuma babu abokantaka, kuma babu ceto. Kafirai kuwa su ne azzalumai

(255) Allah, babu wani abin bauta wa da cancanta sai Shi, Rayayye, Tsayayye da Zatinsa; gyangyaɗi ba ya kama shi, ballantana barci. Abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nasa ne shi kaɗai. Wane ne ya isa ya yi ceto a wurinsa in ba da izininsa ba? Ya san abin da yake tare da su a yanzu da kuma abin da zai biyo bayansu; kuma ba sa iya sanin wani abu cikin iliminsa sai abin da Ya ga dama. Kursiyyunsa ya yalwaci sammai da ƙasa, kuma kiyaye su ba zai nauyaye Shi ba, kuma Shi ne Maɗaukaki Mai girma

(256) Babu tilastawa a addini, haƙiƙa shiriya ta riga ta bayyana daban da ɓata. Don haka duk wanda ya kafirce wa Dagutu, kuma ya yi imani da Allah, to haƙiƙa ya yi riƙo da igiya mafi ƙarfi wadda ba ta tsinkewa. Kuma Allah Mai ji ne, Masani

ٱللَّهُ وَلِيُّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ يُخْرِجُهُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ ۖ
وَٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ أَوْلِيَآؤُهُمُ ٱلطَّٰغُوتُ يُخْرِجُونَهُم مِّنَ
ٱلنُّورِ إِلَى ٱلظُّلُمَٰتِ ۗ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ ۖ هُمْ فِيهَا
خَٰلِدُونَ ﴿٢٥٧﴾ أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِى حَآجَّ إِبْرَٰهِـۧمَ فِى رَبِّهِۦٓ
أَنْ ءَاتَىٰهُ ٱللَّهُ ٱلْمُلْكَ إِذْ قَالَ إِبْرَٰهِـۧمُ رَبِّىَ ٱلَّذِى يُحْىِۦ
وَيُمِيتُ قَالَ أَنَا۠ أُحْىِۦ وَأُمِيتُ ۖ قَالَ إِبْرَٰهِـۧمُ فَإِنَّ ٱللَّهَ يَأْتِى
بِٱلشَّمْسِ مِنَ ٱلْمَشْرِقِ فَأْتِ بِهَا مِنَ ٱلْمَغْرِبِ فَبُهِتَ ٱلَّذِى
كَفَرَ ۗ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٢٥٨﴾ أَوْ كَٱلَّذِى
مَرَّ عَلَىٰ قَرْيَةٍ وَهِىَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا قَالَ أَنَّىٰ يُحْىِۦ
هَٰذِهِ ٱللَّهُ بَعْدَ مَوْتِهَا ۖ فَأَمَاتَهُ ٱللَّهُ مِا۟ئَةَ عَامٍ ثُمَّ بَعَثَهُۥ ۖ
قَالَ كَمْ لَبِثْتَ ۖ قَالَ لَبِثْتُ يَوْمًا أَوْ بَعْضَ يَوْمٍ ۖ قَالَ بَل
لَّبِثْتَ مِا۟ئَةَ عَامٍ فَٱنظُرْ إِلَىٰ طَعَامِكَ وَشَرَابِكَ لَمْ يَتَسَنَّهْ ۖ
وَٱنظُرْ إِلَىٰ حِمَارِكَ وَلِنَجْعَلَكَ ءَايَةً لِّلنَّاسِ ۖ وَٱنظُرْ إِلَى
ٱلْعِظَامِ كَيْفَ نُنشِزُهَا ثُمَّ نَكْسُوهَا لَحْمًا ۚ فَلَمَّا
تَبَيَّنَ لَهُۥ قَالَ أَعْلَمُ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٢٥٩﴾

(257) Allah Shi ne Majiɓincin lamarin waɗanda suka yi imani, Yana fitar da su daga duffai zuwa ga haske; waɗanda suka kafirce kuwa, majiɓinta lamarinsu su ne ɗagutai, suna fitar da su daga haske zuwa duffai. Waɗannan su ne ‘yan wuta; su masu dawwama ne a cikinta

(258) Shin ba ka ga wanda ya yi jayayya da Ibrahim ba game da lamarin Ubangijinsa, don Allah ya ba shi mulki, yayin da Ibrahimu ya ce: “Ubangijina Shi ne Yake rayawa, kuma Yake kashewa.” Sai ya ce: “Ai ni ma ina rayawa, kuma ina kashewa.” Sai Ibrahim ya ce: “To Allah Yana kawo rana daga gabas, to kai ka kawo ta daga yamma.” Sai wanda ya kafirta ya kiɗime. Kuma Allah ba Ya shiryar da azzaluman mutane

(259) Ko kuma kamar mutumin da ya wuce ta wata alƙarya alhalin ta zama kango, sai ya ce: “Ta yaya Allah zai raya wannan bayan mutuwarta?” Sai Allah Ya karɓi rayuwarsa tsawon shekara ɗari, sannan Ya tashe shi, Ya ce: “Mene ne tsawon lokacin da ka zauna?” Sai ya ce: “Ai na zauna yini ɗaya ne ko ma wani sashi na yinin.” Sai Ya ce: “Ai ka zauna tsawon shekara ɗari ne, don haka dubi abincinka da abin shanka bai canja ba, kuma ka dubi jakinka mana, don Mu sanya ka ka zamanto aya ga mutane, kuma ka dubi ƙasusuwan ka gani yadda za Mu haɗa su, sannan Mu lulluɓe su da nama.”To lokacin da komai ya bayyana a gare shi, sai ya ce: “Na sani lalle Allah Mai iko ne a kan komai.”

وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِـۧمُ رَبِّ أَرِنِى كَيْفَ تُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰ ۖ قَالَ أَوَلَمْ
تُؤْمِن ۖ قَالَ بَلَىٰ وَلَٰكِن لِّيَطْمَئِنَّ قَلْبِى ۖ قَالَ فَخُذْ أَرْبَعَةً مِّنَ
ٱلطَّيْرِ فَصُرْهُنَّ إِلَيْكَ ثُمَّ ٱجْعَلْ عَلَىٰ كُلِّ جَبَلٍ مِّنْهُنَّ جُزْءًا
ثُمَّ ٱدْعُهُنَّ يَأْتِينَكَ سَعْيًا ۚ وَٱعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ
﴿٢٦٠﴾ مَّثَلُ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمْوَٰلَهُمْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ كَمَثَلِ حَبَّةٍ
أَنۢبَتَتْ سَبْعَ سَنَابِلَ فِى كُلِّ سُنۢبُلَةٍ مِّا۟ئَةُ حَبَّةٍ ۗ وَٱللَّهُ
يُضَٰعِفُ لِمَن يَشَآءُ ۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ﴿٢٦١﴾ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ
أَمْوَٰلَهُمْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ثُمَّ لَا يُتْبِعُونَ مَآ أَنفَقُوا۟ مَنًّا وَلَآ
أَذًى لَّهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ
يَحْزَنُونَ ﴿٢٦٢﴾ قَوْلٌ مَّعْرُوفٌ وَمَغْفِرَةٌ خَيْرٌ مِّن صَدَقَةٍ
يَتْبَعُهَآ أَذًى ۗ وَٱللَّهُ غَنِىٌّ حَلِيمٌ ﴿٢٦٣﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟
لَا تُبْطِلُوا۟ صَدَقَٰتِكُم بِٱلْمَنِّ وَٱلْأَذَىٰ كَٱلَّذِى يُنفِقُ مَالَهُۥ
رِئَآءَ ٱلنَّاسِ وَلَا يُؤْمِنُ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ ۖ فَمَثَلُهُۥ كَمَثَلِ
صَفْوَانٍ عَلَيْهِ تُرَابٌ فَأَصَابَهُۥ وَابِلٌ فَتَرَكَهُۥ صَلْدًا ۖ لَّا يَقْدِرُونَ
عَلَىٰ شَىْءٍ مِّمَّا كَسَبُوا۟ ۗ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٦٤﴾

(260) Kuma ka tuna lokacin da Ibrahimu ya ce: “Ya Ubangijina, Ka nuna mini yadda Kake rayar da matattu.” Sai ya ce: “Shin ko ba ka yi imani ba ne?” Ya ce: “A’a, (na yi imani), sai dai ina son zuciyata ta ƙara samun nutsuwa.” Sai Ya ce: “To ka kama tsuntsaye huɗu ka tara su wajenka, sannan ka sanya yanka ɗaya-ɗaya nasu a kan kowane saman dutse, sannan ka kira su; za su zo maka da gaggawa. Kuma ka sani cewa lalle Allah Mabuwayi ne, Mai hikima.”

(261) Misalin waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu a hanyar Allah, kamar misalin ƙwaya ɗaya ce da ta fitar da zangarniya bakwai, a cikinta kowace zangarniya kuma (aka sami) ƙwaya ɗari. Kuma Allah Yana ninninkawa ga wanda Ya ga dama, kuma Allah Mai yalwa ne, Masani

(262) Waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu a hanyar Allah, sannan ba sa bin abin da suka ciyar da gori ko cuta, (waɗannan) suna da ladansu a wajen Ubangijinsu, kuma babu tsoro a tare da su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba

(263) Kyakkyawar magana da yafiya sun fi sadakar da cutarwa za ta biyo bayanta alheri. Kuma Allah Shi ne Wadatacce, Mai haƙuri

(264) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ɓata sadaƙoƙinku da gori da cutarwa, kamar wanda yake ciyar da dukiyarsa don mutane su gani, kuma ba ya imani da Allah da ranar lahira; to misalinsa kamar misalin kamfa ne da turɓaya take a kansa sai ruwan sama mamako ya same shi, sai ya bar shi tatas. Ba za su amfana da komai daga abin da suka aikata ba. Kuma Allah ba Ya shiryar da mutane kafirai

وَمَثَلُ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمۡوَٰلَهُمُ ٱبۡتِغَآءَ مَرۡضَاتِ ٱللَّهِ
وَتَثۡبِيتٗا مِّنۡ أَنفُسِهِمۡ كَمَثَلِ جَنَّةِۭ بِرَبۡوَةٍ أَصَابَهَا وَابِلٞ
فَـَٔاتَتۡ أُكُلَهَا ضِعۡفَيۡنِ فَإِن لَّمۡ يُصِبۡهَا وَابِلٞ فَطَلّٞۗ
وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿٢٦٥﴾ أَيَوَدُّ أَحَدُكُمۡ أَن تَكُونَ لَهُۥ
جَنَّةٞ مِّن نَّخِيلٖ وَأَعۡنَٰبٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ لَهُۥ
فِيهَا مِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ وَأَصَابَهُ ٱلۡكِبَرُ وَلَهُۥ ذُرِّيَّةٞ
ضُعَفَآءُ فَأَصَابَهَآ إِعۡصَارٞ فِيهِ نَارٞ فَٱحۡتَرَقَتۡۗ كَذَٰلِكَ
يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلۡأٓيَٰتِ لَعَلَّكُمۡ تَتَفَكَّرُونَ ﴿٢٦٦﴾ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَنفِقُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا كَسَبۡتُمۡ وَمِمَّآ أَخۡرَجۡنَا
لَكُم مِّنَ ٱلۡأَرۡضِۖ وَلَا تَيَمَّمُواْ ٱلۡخَبِيثَ مِنۡهُ تُنفِقُونَ
وَلَسۡتُم بِـَٔاخِذِيهِ إِلَّآ أَن تُغۡمِضُواْ فِيهِۚ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ غَنِيٌّ
حَمِيدٌ ﴿٢٦٧﴾ ٱلشَّيۡطَٰنُ يَعِدُكُمُ ٱلۡفَقۡرَ وَيَأۡمُرُكُم بِٱلۡفَحۡشَآءِۖ
وَٱللَّهُ يَعِدُكُم مَّغۡفِرَةٗ مِّنۡهُ وَفَضۡلٗاۗ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٞ
﴿٢٦٨﴾ يُؤۡتِي ٱلۡحِكۡمَةَ مَن يَشَآءُۚ وَمَن يُؤۡتَ ٱلۡحِكۡمَةَ فَقَدۡ
أُوتِيَ خَيۡرٗا كَثِيرٗاۗ وَمَا يَذَّكَّرُ إِلَّآ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ﴿٢٦٩﴾

(265) Kuma misalin waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu don neman yardar Allah da tabbatar da (imani) a zukatansu, kamar misalin gona ce a kan jigawa sai ruwan sama mamako ya same ta, sai ta ba da amfaninta riɓi-biyu. To idan mamakon ruwan bai same ta ba, sai yayyafi (ya wadatar da ita). Kuma Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne

(266) Shin yanzu ɗayanku zai yi fatan a ce yana da wata gona ta itacen dabino da kuma inabai, wadda ƙoramu suke gudana a ƙarƙashinta, yana da dukkan wasu nau'uka na 'ya'yan itace a cikinta, sai kuma girma ya kama shi, kuma ga shi yana da yara raunana, sai kuma wata irin guguwa mai ɗauke da wuta ta same ta, sai (gonar gaba ɗaya) ta ƙone? Kamar haka ne Allah Yake bayyana muku ayoyi don ku rifka yin tunani

(267) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ciyar daga daɗaɗan abin da kuka tsuwurwuta da kuma abin da muka fitar muku shi daga cikin ƙasa, kuma kar ku nufaci mummuna daga cikinsa ku ce daga gare shi ne za ku ciyar, alhalin ku ma kanku (idan an ba ku) ba za ku karɓe shi ba sai kun runtse idanu. Kuma ku sani cewa lalle Allah Mawadaci ne, Sha-yabo

(268) Shaiɗan ne yake tsoratar da ku da talauci, kuma yana umartar ku da alfasha; Allah kuwa Yana yi muku alƙawarin gafara ta musamman daga gare Shi da kuma falala. Kuma Allah Mai yalwa ne, Masani

(269) Yana bayar da hikima ga wanda Ya ga dama; kuma dukkan wanda aka bai wa hikima, to haƙiƙa an ba shi alheri mai tarin yawa. Kuma ba wanda yake wa'azantuwa sai ma'abota hankula

وَمَآ أَنفَقْتُم مِّن نَّفَقَةٍ أَوْ نَذَرْتُم مِّن نَّذْرٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ
يَعْلَمُهُۥ ۗ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنْ أَنصَارٍ ﴿٢٧٠﴾ إِن تُبْدُوا۟
ٱلصَّدَقَٰتِ فَنِعِمَّا هِىَ ۖ وَإِن تُخْفُوهَا وَتُؤْتُوهَا
ٱلْفُقَرَآءَ فَهُوَ خَيْرٌ لَّكُمْ ۚ وَيُكَفِّرُ عَنكُم مِّن
سَيِّـَٔاتِكُمْ ۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ﴿٢٧١﴾ ۞ لَّيْسَ
عَلَيْكَ هُدَىٰهُمْ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَهْدِى مَن يَشَآءُ ۗ وَمَا
تُنفِقُوا۟ مِنْ خَيْرٍ فَلِأَنفُسِكُمْ ۚ وَمَا تُنفِقُونَ إِلَّا
ٱبْتِغَآءَ وَجْهِ ٱللَّهِ ۚ وَمَا تُنفِقُوا۟ مِنْ خَيْرٍ يُوَفَّ إِلَيْكُمْ
وَأَنتُمْ لَا تُظْلَمُونَ ﴿٢٧٢﴾ لِلْفُقَرَآءِ ٱلَّذِينَ أُحْصِرُوا۟
فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ لَا يَسْتَطِيعُونَ ضَرْبًا فِى ٱلْأَرْضِ
يَحْسَبُهُمُ ٱلْجَاهِلُ أَغْنِيَآءَ مِنَ ٱلتَّعَفُّفِ تَعْرِفُهُم
بِسِيمَٰهُمْ لَا يَسْـَٔلُونَ ٱلنَّاسَ إِلْحَافًا ۗ وَمَا تُنفِقُوا۟ مِنْ
خَيْرٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ بِهِۦ عَلِيمٌ ﴿٢٧٣﴾ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمْوَٰلَهُم
بِٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ سِرًّا وَعَلَانِيَةً فَلَهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ
رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٢٧٤﴾

(270) Kuma abin da kuka ciyar na abin ciyarwa ko kuka yi alwashi na bakance, to lalle Allah Yana sane da shi. Kuma azzalumai ba su da waɗansu mataimaka

(271) In da za ku bayyanar da sadakoki a fili, to madalla da hakan, kuma idan kuka ɓoye sadaƙar, kuma kuka ba da ita ga talakawa, to hakan shi ya fi alheri a gare ku, kuma zai kankare muku kurakurenku, kuma Allah Masanin abin da kuke aikatawa ne

(272) Shiryar da su ba a kanka yake ba, sai dai Allah ne Yake shiryar da wanda Ya ga dama, kuma duk abin da kuka ciyar na alheri, to domin kawunanku ne, kuma ba za ku ciyar ba sai don neman yardar Allah; kuma duk abin da kuka ciyar na alheri, za a cika muku ladansa, alhali kuma ba za a zalunce ku ba

(273) Ga mabuƙata waɗanda aka tsare saboda Allah, ba su da ikon yawatawa a bayan ƙasa, har wanda ya jahilci halinsu yana zato su mawadata ne saboda kame kai; za ka gane su ne da alamominsu, ba sa naciyar roƙar mutane, kuma duk abin da kuka ciyar na alheri, to Allah Yana sane da shi

(274) Waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu dare da rana a ɓoye da kuma a sarari, to suna da ladansu a wajen Ubangijinsu, kuma babu tsoro a tare da su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba

ٱلَّذِينَ يَأۡكُلُونَ ٱلرِّبَوٰاْ لَا يَقُومُونَ إِلَّا كَمَا يَقُومُ ٱلَّذِي
يَتَخَبَّطُهُ ٱلشَّيۡطَٰنُ مِنَ ٱلۡمَسِّۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَالُوٓاْ إِنَّمَا ٱلۡبَيۡعُ
مِثۡلُ ٱلرِّبَوٰاْۗ وَأَحَلَّ ٱللَّهُ ٱلۡبَيۡعَ وَحَرَّمَ ٱلرِّبَوٰاْۚ فَمَن جَآءَهُۥ
مَوۡعِظَةٞ مِّن رَّبِّهِۦ فَٱنتَهَىٰ فَلَهُۥ مَا سَلَفَ وَأَمۡرُهُۥٓ إِلَى ٱللَّهِۖ وَمَنۡ
عَادَ فَأُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٢٧٥ يَمۡحَقُ
ٱللَّهُ ٱلرِّبَوٰاْ وَيُرۡبِي ٱلصَّدَقَٰتِۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ كُلَّ كَفَّارٍ أَثِيمٍ
٢٧٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ
وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ لَهُمۡ أَجۡرُهُمۡ عِندَ رَبِّهِمۡ وَلَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ
وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ٢٧٧ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ
وَذَرُواْ مَا بَقِيَ مِنَ ٱلرِّبَوٰٓاْ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٢٧٨ فَإِن لَّمۡ تَفۡعَلُواْ
فَأۡذَنُواْ بِحَرۡبٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦۖ وَإِن تُبۡتُمۡ فَلَكُمۡ رُءُوسُ
أَمۡوَٰلِكُمۡ لَا تَظۡلِمُونَ وَلَا تُظۡلَمُونَ ٢٧٩ وَإِن كَانَ
ذُو عُسۡرَةٖ فَنَظِرَةٌ إِلَىٰ مَيۡسَرَةٖۚ وَأَن تَصَدَّقُواْ خَيۡرٞ لَّكُمۡ
إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٢٨٠ وَٱتَّقُواْ يَوۡمٗا تُرۡجَعُونَ فِيهِ إِلَى
ٱللَّهِۖ ثُمَّ تُوَفَّىٰ كُلُّ نَفۡسٖ مَّا كَسَبَتۡ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ٢٨١

(275) Waɗanda suke cin riba ba za su tashi ba (daga ƙaburburansu) sai kamar tashin mutumin da Shaiɗan yake bige shi da hauka. Hakan zai faru ne don sun ce: “Lalle kasuwanci kamar riba yake.” Kuma Allah Ya halatta kasuwanci, kuma Ya haramta riba. To duk wanda wa’azi ya zo masa daga wurin Ubangijinsa, sai ya daina, to abin da ya wuce a baya ya zama nasa, kuma al’amarinsa yana wurin Allah; wanda kuma ya sake komawa daga baya, to waɗannan su ne ma’abota wuta, suna masu dawwama a cikinta

(276) Allah Yana shafe albarkar riba, Yana kuma haɓaka sadaƙa. Kuma Allah ba Ya son dukkan wani mai yawan kafircewa, mai yawan saɓo

(277) Lalle waɗanda suka yi imani kuma suka yi ayyuka nagari kuma suka tsayar da salla, kuma suka bayar da zakka, to suna da ladansu a wajen Ubangijinsu, kuma babu jin tsoro a gare su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba

(278) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku rabu da abin da ya yi ragowa na riba in har kun kasance muminai

(279) Idan kuwa ba ku aikata haka ba, to ku saurari wani yaƙi daga Allah da Manzonsa; idan kuwa kun tuba, to uwar kuɗin taku ce, ba za ku yi zalunci ba, ku ma kuma ba za a zalunce ku ba


(280) Kuma idan (mai cin bashin) ya kasance ma’abocin matsi, to sai a yi masa jinkiri zuwa lokacin da zai sami sauƙi, kuma in da za ku yi sadaƙa shi ya fi alheri a gare ku in kun kasance kuna da masaniya

(281) Kuma ku kiyayi wani yini da za a mayar da ku zuwa ga Allah a cikinsa, sannan kowane rai za a cika masa abin da ya aiwatar na aiki, kuma su ba za a zalunce su ba

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا تَدَايَنتُم بِدَيۡنٍ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗى
فَٱكۡتُبُوهُۚ وَلۡيَكۡتُب بَّيۡنَكُمۡ كَاتِۢبُۢ بِٱلۡعَدۡلِۚ وَلَا يَأۡبَ
كَاتِۢبٌ أَن يَكۡتُبَ كَمَا عَلَّمَهُ ٱللَّهُۚ فَلۡيَكۡتُبۡ وَلۡيُمۡلِلِ
ٱلَّذِي عَلَيۡهِ ٱلۡحَقُّ وَلۡيَتَّقِ ٱللَّهَ رَبَّهُۥ وَلَا يَبۡخَسۡ مِنۡهُ شَيۡـٔٗاۚ
فَإِن كَانَ ٱلَّذِي عَلَيۡهِ ٱلۡحَقُّ سَفِيهًا أَوۡ ضَعِيفًا أَوۡ لَا يَسۡتَطِيعُ
أَن يُمِلَّ هُوَ فَلۡيُمۡلِلۡ وَلِيُّهُۥ بِٱلۡعَدۡلِۚ وَٱسۡتَشۡهِدُواْ شَهِيدَيۡنِ
مِن رِّجَالِكُمۡۖ فَإِن لَّمۡ يَكُونَا رَجُلَيۡنِ فَرَجُلٞ وَٱمۡرَأَتَانِ
مِمَّن تَرۡضَوۡنَ مِنَ ٱلشُّهَدَآءِ أَن تَضِلَّ إِحۡدَىٰهُمَا فَتُذَكِّرَ
إِحۡدَىٰهُمَا ٱلۡأُخۡرَىٰۚ وَلَا يَأۡبَ ٱلشُّهَدَآءُ إِذَا مَا دُعُواْۚ وَلَا تَسۡـَٔمُوٓاْ
أَن تَكۡتُبُوهُ صَغِيرًا أَوۡ كَبِيرًا إِلَىٰٓ أَجَلِهِۦۚ ذَٰلِكُمۡ أَقۡسَطُ
عِندَ ٱللَّهِ وَأَقۡوَمُ لِلشَّهَٰدَةِ وَأَدۡنَىٰٓ أَلَّا تَرۡتَابُوٓاْ إِلَّآ أَن تَكُونَ
تِجَٰرَةً حَاضِرَةٗ تُدِيرُونَهَا بَيۡنَكُمۡ فَلَيۡسَ عَلَيۡكُمۡ جُنَاحٌ
أَلَّا تَكۡتُبُوهَاۗ وَأَشۡهِدُوٓاْ إِذَا تَبَايَعۡتُمۡۚ وَلَا يُضَآرَّ كَاتِۢبٞ
وَلَا شَهِيدٞۚ وَإِن تَفۡعَلُواْ فَإِنَّهُۥ فُسُوقُۢ بِكُمۡۗ وَٱتَّقُواْ
ٱللَّهَۖ وَيُعَلِّمُكُمُ ٱللَّهُۗ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ٢٨٢

(282) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka ba wa junanku bashi zuwa wani lokaci sananne, to ku rubuta shi, kuma a sami wani marubuci da zai rubuta a tsakaninku da adalci, kuma marubucin kar ya ƙi rubutawa kamar yadda Allah ya sanar da shi. Don haka ya rubuta, kuma shi wanda haƙƙi yake kansa sai ya yi shifta gare shi, kuma ya ji tsoron Allah Ubangijinsa, kuma kada ya tauye wani abu a cikinsa. To idan wanda haƙƙi yake kansa ya kasance wawa ne ko mai rauni ko ba shi da ikon ya yi shifta shi da kansa, to sai majiɓincin lamarinsa ya yi shifta (a madadinsa) da adalci. Kuma ku kafa shaidu biyu cikin mazajenku; kuma idan ba su kasance mazaje biyu ba, to sai a nemi namiji ɗaya da mata biyu daga shaidun da kuka yarda da su, saboda idan ɗaya daga cikinsu ta manta sai ɗayar ta tuna mata, kuma kada shaidun su ƙi zuwa idan an kiraye su, kuma kada ku ƙosa, ku rubuta shi, kaɗan ne ko da yawa, zuwa cikar wa'adinsa. Abin da aka ambata mukun nan shi ne ya fi zama adalci a wajen Allah, kuma ya fi daidaita shaida, kuma shi ya fi kusata ku ta yadda ba za ku yi shakka ba, sai dai idan ya kasance ciniki ne hannu da hannu da kuke gudanar da shi tsakaninku; to babu laifi a kanku idan ba ku rubuta shi ba. Kuma ku kafa shaida idan kun yi hulɗa ta ciniki, kuma kada marubuci ya yi cuta, haka shi ma mai shaida (kada ya yi cuta)[1]. Idan kuwa har kuka aikata haka, to lalle wannan fasiƙanci ne a gare ku. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma Allah Yana sanar da ku (dokokinsa). Kuma Allah Masanin komai ne

(1) Hakanan ayar tana nufin cewa, su ma kuma kada a cutar da su.


* وَإِن كُنتُمْ عَلَىٰ سَفَرٍ وَلَمْ تَجِدُوا۟ كَاتِبًا فَرِهَٰنٌ مَّقْبُوضَةٌ ۖ
فَإِنْ أَمِنَ بَعْضُكُم بَعْضًا فَلْيُؤَدِّ ٱلَّذِى ٱؤْتُمِنَ أَمَٰنَتَهُۥ وَلْيَتَّقِ
ٱللَّهَ رَبَّهُۥ ۗ وَلَا تَكْتُمُوا۟ ٱلشَّهَٰدَةَ ۚ وَمَن يَكْتُمْهَا فَإِنَّهُۥٓ
ءَاثِمٌ قَلْبُهُۥ ۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ عَلِيمٌ ﴿٢٨٣﴾ لِّلَّهِ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۗ وَإِن تُبْدُوا۟ مَا فِىٓ أَنفُسِكُمْ أَوْ تُخْفُوهُ
يُحَاسِبْكُم بِهِ ٱللَّهُ ۖ فَيَغْفِرُ لِمَن يَشَآءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ ۗ
وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٢٨٤﴾ ءَامَنَ ٱلرَّسُولُ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيْهِ
مِن رَّبِّهِۦ وَٱلْمُؤْمِنُونَ ۚ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ
وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيْنَ أَحَدٍ مِّن رُّسُلِهِۦ ۚ وَقَالُوا۟
سَمِعْنَا وَأَطَعْنَا ۖ غُفْرَانَكَ رَبَّنَا وَإِلَيْكَ ٱلْمَصِيرُ ﴿٢٨٥﴾ لَا يُكَلِّفُ
ٱللَّهُ نَفْسًا إِلَّا وُسْعَهَا ۚ لَهَا مَا كَسَبَتْ وَعَلَيْهَا مَا ٱكْتَسَبَتْ ۗ
رَبَّنَا لَا تُؤَاخِذْنَآ إِن نَّسِينَآ أَوْ أَخْطَأْنَا ۚ رَبَّنَا وَلَا تَحْمِلْ
عَلَيْنَآ إِصْرًا كَمَا حَمَلْتَهُۥ عَلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِنَا ۚ رَبَّنَا
وَلَا تُحَمِّلْنَا مَا لَا طَاقَةَ لَنَا بِهِۦ ۖ وَٱعْفُ عَنَّا وَٱغْفِرْ لَنَا
وَٱرْحَمْنَآ ۚ أَنتَ مَوْلَىٰنَا فَٱنصُرْنَا عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٨٦﴾

(283) Kuma idan kun kasance a halin tafiya, kuma ba ku sami marubuci ba, to sai a ba da jingina da za a karɓa, kuma idan sashinku ya amince wa sashi, to shi wanda aka amincewan ya bayar da amanarsa, kuma ya kiyayi Allah Ubangijinsa. Kuma kada ku ɓoye shaida; duk wanda ya ɓoye ta kuwa, to lalle shi zuciyarsa a cike take da saɓo. Kuma Allah Masanin abin da kuke aikatawa ne

(284) Duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa na Allah ne. Kuma in har kuka bayyana abin da yake cikin zukatanku ko kuka ɓoye shi, Allah zai yi muku hisabi a kansa, sai Ya yi gafara ga wanda Ya ga dama, Ya kuma yi azaba ga wanda Ya ga dama. Kuma Allah Mai iko ne a kan komai

(285) Manzon ya yi imani da abin da aka saukar masa daga Ubangijinsa, muminai ma haka, kowanne ya yi imani da Allah da mala'ikunsa da littattafansa da manzanninsa, (suna cewa) : "Ba ma nuna bambanci tsakanin ɗaya daga cikin manzanninsa." Kuma suka ce: "Mun ji kuma mun bi ; muna neman gafararka ya Ubangijinmu, kuma zuwa gare Ka ne makoma take

(286) Allah ba Ya kallafa wa rai sai abin da zai iya. Abin da ya aikata (na alheri) nasa ne, hakanan sakamakon abin da ya aikata (na sharri) shi ma nasa ne. Ya Ubangijinmu, kada Ka riƙe mu da laifi idan mun yi mantuwa ko mun yi kuskure. Ya Ubangijinmu, kada kuma Ka ɗora mana wani nauyi irin wanda ka ɗora wa waɗanda suke gabaninmu. Ya Ubangijinmu, kada kuma Ka ɗora mana abin da ba mu da iko a kansa, kuma Ka yi mana afuwa, kuma Ka yi mana gafara, kuma Ka ji ƙan mu; Kai ne Majiɓincin lamarinmu, don haka Ka taimake mu a kan mutane kafirai



Sura Ali-Imran

سُورَةُ آلِ عِمْرَانَ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

الٓمٓ ﴿١﴾ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْحَىُّ ٱلْقَيُّومُ ﴿٢﴾ نَزَّلَ عَلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ
بِٱلْحَقِّ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ وَأَنزَلَ ٱلتَّوْرَىٰةَ وَٱلْإِنجِيلَ ﴿٣﴾ مِن
قَبْلُ هُدًى لِّلنَّاسِ وَأَنزَلَ ٱلْفُرْقَانَ ۗ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ
لَهُمْ عَذَابٌ شَدِيدٌ ۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ ذُو ٱنتِقَامٍ ﴿٤﴾ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَخْفَىٰ
عَلَيْهِ شَىْءٌ فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا فِى ٱلسَّمَآءِ ﴿٥﴾ هُوَ ٱلَّذِى يُصَوِّرُكُمْ
فِى ٱلْأَرْحَامِ كَيْفَ يَشَآءُ ۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٦﴾ هُوَ
ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ عَلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ مِنْهُ ءَايَٰتٌ مُّحْكَمَٰتٌ هُنَّ أُمُّ
ٱلْكِتَٰبِ وَأُخَرُ مُتَشَٰبِهَٰتٌ ۖ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِمْ زَيْغٌ فَيَتَّبِعُونَ
مَا تَشَٰبَهَ مِنْهُ ٱبْتِغَآءَ ٱلْفِتْنَةِ وَٱبْتِغَآءَ تَأْوِيلِهِۦ ۖ وَمَا يَعْلَمُ تَأْوِيلَهُۥٓ
إِلَّا ٱللَّهُ ۗ وَٱلرَّٰسِخُونَ فِى ٱلْعِلْمِ يَقُولُونَ ءَامَنَّا بِهِۦ كُلٌّ مِّنْ عِندِ
رَبِّنَا ۗ وَمَا يَذَّكَّرُ إِلَّآ أُو۟لُوا۟ ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿٧﴾ رَبَّنَا لَا تُزِغْ قُلُوبَنَا بَعْدَ
إِذْ هَدَيْتَنَا وَهَبْ لَنَا مِن لَّدُنكَ رَحْمَةً ۚ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْوَهَّابُ ﴿٨﴾ رَبَّنَآ
إِنَّكَ جَامِعُ ٱلنَّاسِ لِيَوْمٍ لَّا رَيْبَ فِيهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُخْلِفُ ٱلْمِيعَادَ ﴿٩﴾

(1) ALIF LAAM MIIM[1].
(2) Allah, babu wani abin bautawa da gaskiya sai Shi, Shi Rayayye ne, Tsayayye da Zatinsa
(3) Ya saukar maka da Littafi da gaskiya, yana mai gaskata abin da ya gabace shi, kuma Ya saukar da Attaura da Linjila
(4) Tun kafin (Alƙur'ani), (don su zama) shiriya ga mutane, kuma Ya saukar da mai rarrabewa (tsakanin ƙarya da gaskiya). Lalle waɗanda suka kafirce wa ayoyin Allah, suna da azaba mai tsanani, kuma Allah Mabuwayi ne, Ma'abocin ɗaukar fansa
(5) Lalle Allah babu abin da yake ɓoyuwa a gare Shi a ƙasa ko a sama
(6) Shi ne wanda Yake suranta ku a cikin mahaifu irin yadda Ya ga dama, babu abin bauta wa da gaskiya sai Shi, Shi ne Mabuwayi, Mai hikima
(7) Shi ne Wanda ya saukar maka da Littafi, a cikinsa akwai ayoyi masu bayyanannun hukunce-hukunce, su ne asalin Littafin, akwai kuma waɗansu masu rikitarwa[1]; to amma waɗanda suke da karkata a zukatansu sai su rika bin abin da yake rikitarwar a cikinsu don neman fitina da kuma neman sanin haƙiƙanin fassararsa. Kuma babu wanda ya san haƙiƙanin fassararsa sai Allah. Kuma masu zurfi cikin ilimi suna cewa: "Mun yi imani da shi, dukkaninsa daga wurin Ubangijinmu yake." Kuma ba mai wa'azantuwa sai masu hankali
(8) "Ya Ubangijinmu, kada Ka karkatar da zukatanmu bayan Ka shiryar da mu, kuma Ka yi mana rahama daga gare Ka. Lalle kai Mai yawan baiwa ne."
(9) "Ya Ubangijinmu, lalle Kai ne Mai tattara mutane a yinin da babu kokwanto a cikinsa. Lalle Allah ba Ya saɓa alƙawari."

(1) Ayoyi masu rikitarwa, su ne waɗanda ma'anoninsu ba su fito fili ba.

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَن تُغۡنِيَ عَنۡهُمۡ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُم
مِّنَ ٱللَّهِ شَيۡـٔٗاۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ وَقُودُ ٱلنَّارِ ١٠ كَدَأۡبِ ءَالِ
فِرۡعَوۡنَ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ
بِذُنُوبِهِمۡۗ وَٱللَّهُ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ١١ قُل لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ
سَتُغۡلَبُونَ وَتُحۡشَرُونَ إِلَىٰ جَهَنَّمَۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمِهَادُ ١٢
قَدۡ كَانَ لَكُمۡ ءَايَةٞ فِي فِئَتَيۡنِ ٱلۡتَقَتَاۖ فِئَةٞ تُقَٰتِلُ فِي
سَبِيلِ ٱللَّهِ وَأُخۡرَىٰ كَافِرَةٞ يَرَوۡنَهُم مِّثۡلَيۡهِمۡ رَأۡيَ
ٱلۡعَيۡنِۚ وَٱللَّهُ يُؤَيِّدُ بِنَصۡرِهِۦ مَن يَشَآءُۗ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَعِبۡرَةٗ لِّأُوْلِي ٱلۡأَبۡصَٰرِ ١٣ زُيِّنَ لِلنَّاسِ حُبُّ ٱلشَّهَوَٰتِ
مِنَ ٱلنِّسَآءِ وَٱلۡبَنِينَ وَٱلۡقَنَٰطِيرِ ٱلۡمُقَنطَرَةِ مِنَ ٱلذَّهَبِ
وَٱلۡفِضَّةِ وَٱلۡخَيۡلِ ٱلۡمُسَوَّمَةِ وَٱلۡأَنۡعَٰمِ وَٱلۡحَرۡثِۗ ذَٰلِكَ
مَتَٰعُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ وَٱللَّهُ عِندَهُۥ حُسۡنُ ٱلۡمَـَٔابِ ١٤ ۞ قُلۡ
أَؤُنَبِّئُكُم بِخَيۡرٖ مِّن ذَٰلِكُمۡۖ لِلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ عِندَ رَبِّهِمۡ
جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَأَزۡوَٰجٞ
مُّطَهَّرَةٞ وَرِضۡوَٰنٞ مِّنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ بَصِيرُۢ بِٱلۡعِبَادِ ١٥

(10) Lalle wadanda suka kafirta, dukiyoyinsu da ‘ya’yansu ba za su wadatar da su da komai ba a wajen Allah; kuma wadannan su makamashi ne na wuta

(11) Kamar dai halin abin da ya gudana ga mutanen Fir’auna da wadanda suka gabace su. Sun karyata ayoyinmu, sai Allah Ya kama su da zunubansu, kuma Allah Mai tsananin ukuba ne

(12) Ka ce wa wadanda suka kafirta: “Da sannu za a rinjaye ku, kuma za a tara ku zuwa Jahannama. Kuma tir da wannan mashimfidi

(13) Hakika wata izina ta bayyana a gare ku game da wasu rundunoni biyu da suka gwabza, daya rundunar tana yaki saboda Allah, dayar kuma kafira ce, suna kallon su (kafiran) kamar ninki biyu a ganin ido[1]; kuma Allah Yana karfafar wanda Ya ga dama da nasararsa. Lalle a cikin hakan akwai izina ga ma’abota basira

(14) An kawata wa mutane son sha’awace-sha’awace na mata da ‘ya’ya da dukiya mai yawa abar tarawa ta zinariya da azurfa da kuma kiwatattun dawaki da dabbobi na gida da amfanin gona. Wadannan duk morewa ce ta rayuwar duniya; Allah kuwa a wurinsa ne kyakkyawar makoma take

(15) Ka ce: “Shin in ba ku labarin da abin da ya fi wadancan alheri? Wadanda suka yi takawa, suna da wasu gidajen aljanna wadanda koramu suke gudana ta karkashinsu, a wurin Ubangijinsu, suna masu zama a cikinsu dindindin da mata na aure tsarkaka da kuma yarda daga Allah. Kuma Allah Mai ganin bayinsa ne.”

(1) Kungiyar farko su ne Annabi ( ) da sahabbai a lokacin yakin Badar, suna ganin kungiya ta biyu wato kafirai, sun ninka su gida biyu. Wannan kuwa ya kara musu dogaro ga Allah.

الَّذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَآ إِنَّنَآ ءَامَنَّا فَٱغْفِرْ لَنَا ذُنُوبَنَا
وَقِنَا عَذَابَ ٱلنَّارِ ﴿١٦﴾ ٱلصَّٰبِرِينَ وَٱلصَّٰدِقِينَ وَٱلْقَٰنِتِينَ
وَٱلْمُنفِقِينَ وَٱلْمُسْتَغْفِرِينَ بِٱلْأَسْحَارِ ﴿١٧﴾ شَهِدَ ٱللَّهُ
أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَأُو۟لُوا۟ ٱلْعِلْمِ قَآئِمًۢا
بِٱلْقِسْطِ ۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿١٨﴾ إِنَّ ٱلدِّينَ
عِندَ ٱللَّهِ ٱلْإِسْلَٰمُ ۗ وَمَا ٱخْتَلَفَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ
إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلْعِلْمُ بَغْيًۢا بَيْنَهُمْ ۗ وَمَن يَكْفُرْ
بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلْحِسَابِ ﴿١٩﴾ فَإِنْ حَآجُّوكَ
فَقُلْ أَسْلَمْتُ وَجْهِىَ لِلَّهِ وَمَنِ ٱتَّبَعَنِ ۗ وَقُل لِّلَّذِينَ أُوتُوا۟
ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْأُمِّيِّـۧنَ ءَأَسْلَمْتُمْ ۚ فَإِنْ أَسْلَمُوا۟ فَقَدِ ٱهْتَدَوا۟ ۖ
وَّإِن تَوَلَّوْا۟ فَإِنَّمَا عَلَيْكَ ٱلْبَلَٰغُ ۗ وَٱللَّهُ بَصِيرٌۢ بِٱلْعِبَادِ ﴿٢٠﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكْفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَيَقْتُلُونَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ
بِغَيْرِ حَقٍّ وَيَقْتُلُونَ ٱلَّذِينَ يَأْمُرُونَ بِٱلْقِسْطِ مِنَ
ٱلنَّاسِ فَبَشِّرْهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿٢١﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ حَبِطَتْ
أَعْمَٰلُهُمْ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿٢٢﴾

(16) (Su ne) waɗanda suke cewa: “Ya Ubangijinmu, lalle mu mun yi imani, don haka Ka gafarta mana zunubanmu, kuma Ka tserar da mu daga azabar wuta.”

(17) (Su ne) masu haƙuri, masu gaskiya, kuma masu ɗa’a, kuma masu ciyarwa, kuma masu neman gafara a ƙarshen dare

(18) Allah Ya shaida cewa, babu abin bauta wa da gaskiya sai Shi, haka mala’iku ma da ma’abota ilimi, Tsayayye ne da adalci. Babu abin bauta wa da gaskiya sai Shi, Mabuwayi, Mai hikima

(19) Lalle addini a wurin Allah shi ne Musulunci. Kuma waɗanda aka ba wa Littafi ba su yi saɓani ba sai bayan da ilimi ya zo musu saboda zalunci a tsakaninsu. Wanda kuwa duk ya kafirce wa ayoyin Allah, to lalle Allah Mai gaggawar hisabi ne

(20) To idan sun yi jayayya da kai, sai ka ce: “Ni na miƙa wuyana ne ga Allah, haka ma wanda ya bi ni.” Kuma ka faɗa wa waɗanda aka bai wa Littafi da Ummiyyai (Larabawa): “Shin kun miƙa wuya?” To idan sun miƙa wuya, haƙiƙa sun shiryu; idan kuwa suka juya baya, to babu abin da yake a kanka sai isar da saƙo. Kuma Allah Mai ganin bayinsa ne

(21) Lalle waɗanda suke kafirce wa ayoyin Allah, kuma suke kashe annabawa ba tare da wani haƙƙi ba, kuma suke kashe waɗanda suke yin umarni da adalci cikin mutane, to ka yi musu albishir da wata azaba mai raɗaɗi

(22) Waɗannan su ne waɗanda ayyukansu suka lalace a duniya da lahira, kuma ba su da wasu mataimaka

أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ نَصِيبًا مِّنَ ٱلْكِتَٰبِ يُدْعَوْنَ إِلَىٰ كِتَٰبِ
ٱللَّهِ لِيَحْكُمَ بَيْنَهُمْ ثُمَّ يَتَوَلَّىٰ فَرِيقٌ مِّنْهُمْ وَهُم مُّعْرِضُونَ ﴿٢٣﴾
ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَالُوا۟ لَن تَمَسَّنَا ٱلنَّارُ إِلَّآ أَيَّامًا مَّعْدُودَٰتٍ ۖ
وَغَرَّهُمْ فِى دِينِهِم مَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ﴿٢٤﴾ فَكَيْفَ إِذَا جَمَعْنَٰهُمْ
لِيَوْمٍ لَّا رَيْبَ فِيهِ ۖ وَوُفِّيَتْ كُلُّ نَفْسٍ مَّا كَسَبَتْ وَهُمْ
لَا يُظْلَمُونَ ﴿٢٥﴾ قُلِ ٱللَّهُمَّ مَٰلِكَ ٱلْمُلْكِ تُؤْتِى ٱلْمُلْكَ مَن
تَشَآءُ وَتَنزِعُ ٱلْمُلْكَ مِمَّن تَشَآءُ وَتُعِزُّ مَن تَشَآءُ وَتُذِلُّ مَن
تَشَآءُ ۖ بِيَدِكَ ٱلْخَيْرُ ۖ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٢٦﴾ تُولِجُ ٱلَّيْلَ
فِى ٱلنَّهَارِ وَتُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِى ٱلَّيْلِ ۖ وَتُخْرِجُ ٱلْحَىَّ مِنَ ٱلْمَيِّتِ
وَتُخْرِجُ ٱلْمَيِّتَ مِنَ ٱلْحَىِّ ۖ وَتَرْزُقُ مَن تَشَآءُ بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴿٢٧﴾
لَّا يَتَّخِذِ ٱلْمُؤْمِنُونَ ٱلْكَٰفِرِينَ أَوْلِيَآءَ مِن دُونِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ۖ
وَمَن يَفْعَلْ ذَٰلِكَ فَلَيْسَ مِنَ ٱللَّهِ فِى شَىْءٍ إِلَّآ أَن تَتَّقُوا۟ مِنْهُمْ
تُقَىٰةً ۗ وَيُحَذِّرُكُمُ ٱللَّهُ نَفْسَهُۥ ۗ وَإِلَى ٱللَّهِ ٱلْمَصِيرُ ﴿٢٨﴾ قُلْ
إِن تُخْفُوا۟ مَا فِى صُدُورِكُمْ أَوْ تُبْدُوهُ يَعْلَمْهُ ٱللَّهُ ۗ وَيَعْلَمُ
مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٢٩﴾

(23) Shin ba ka ga waɗannan da aka ba su wani kaso na ilimin Littafi ba, ana kiran su zuwa ga Littafin Allah don Ya yi hukunci a tsakaninsu, sannan sai wani ɓangare daga cikinsu suna juya baya, suna masu bijirewa

(24) Wannan kuwa saboda su sun ce: "Wuta ba za ta shafe mu ba sai a waɗansu 'yan kwanaki ƙididdigaggu." kuma abin da suka kasance suna ƙirƙira a addininsu shi ne ya ruɗe su

(25) To yaya halinsu zai kasance idan Muka tara su a wani yini da babu shakka game da shi, kuma kowane rai za a saka masa da abin da ya aikata, kuma su ba za a zalunce su ba?

(26) Ka ce: "Ya Allah, Kai ne Mamallakin mulki, Kana bayar da mulki ga wanda Ka ga dama, kuma Kana ƙwace mulki daga wanda Ka ga dama, kuma Kana ɗaukaka wanda Ka ga dama, kuma Kana ƙasƙantar da wanda Ka ga dama; duk alheri yana hannuka, lalle Kai Mai iko ne a kan komai

(27) "Kana shigar da dare a cikin yini, kuma Kana shigar da yini a cikin dare, kuma Kana fitar da mai rai daga cikin matacce, kuma Kana fitar da matacce daga cikin mai rai; kuma Kana arzurta wanda Ka ga dama ba tare da lissafi ba." (28) Kada muminai su riƙi kafirai a matsayin masoya su ƙyale muminai; duk wanda kuwa ya aikata haka, to shi ba komai ne ba a wurin Allah, sai dai in don ku kare kanku ne daga gare su. Kuma Allah Yana tsoratar da ku kansa. Kuma zuwa ga Allah makoma take

(29) Ka ce: "In za ku ɓoye abin da yake cikin ƙirazanku ko kuma ku bayyana shi, Allah Ya san shi, kuma Yana sane da abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa. Kuma Allah Mai iko ne a kan komai."

يَوْمَ تَجِدُ كُلُّ نَفْسٍ مَّا عَمِلَتْ مِنْ خَيْرٍ مُّحْضَرًا وَمَا عَمِلَتْ
مِن سُوٓءٍ تَوَدُّ لَوْ أَنَّ بَيْنَهَا وَبَيْنَهُۥٓ أَمَدًۢا بَعِيدًا ۗ وَيُحَذِّرُكُمُ ٱللَّهُ
نَفْسَهُۥ ۗ وَٱللَّهُ رَءُوفٌۢ بِٱلْعِبَادِ ﴿٣٠﴾ قُلْ إِن كُنتُمْ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ
فَٱتَّبِعُونِى يُحْبِبْكُمُ ٱللَّهُ وَيَغْفِرْ لَكُمْ ذُنُوبَكُمْ ۗ وَٱللَّهُ غَفُورٌ
رَّحِيمٌ ﴿٣١﴾ قُلْ أَطِيعُوا۟ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ ۖ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ
ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٣٢﴾ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ ٱصْطَفَىٰٓ ءَادَمَ وَنُوحًا وَءَالَ إِبْرَٰهِيمَ
وَءَالَ عِمْرَٰنَ عَلَى ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٣٣﴾ ذُرِّيَّةًۢ بَعْضُهَا مِنۢ بَعْضٍ ۗ وَٱللَّهُ
سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٣٤﴾ إِذْ قَالَتِ ٱمْرَأَتُ عِمْرَٰنَ رَبِّ إِنِّى نَذَرْتُ لَكَ
مَا فِى بَطْنِى مُحَرَّرًا فَتَقَبَّلْ مِنِّىٓ ۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٣٥﴾
فَلَمَّا وَضَعَتْهَا قَالَتْ رَبِّ إِنِّى وَضَعْتُهَآ أُنثَىٰ وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا وَضَعَتْ
وَلَيْسَ ٱلذَّكَرُ كَٱلْأُنثَىٰ ۖ وَإِنِّى سَمَّيْتُهَا مَرْيَمَ وَإِنِّىٓ أُعِيذُهَا بِكَ
وَذُرِّيَّتَهَا مِنَ ٱلشَّيْطَٰنِ ٱلرَّجِيمِ ﴿٣٦﴾ فَتَقَبَّلَهَا رَبُّهَا بِقَبُولٍ
حَسَنٍ وَأَنۢبَتَهَا نَبَاتًا حَسَنًا وَكَفَّلَهَا زَكَرِيَّا ۖ كُلَّمَا دَخَلَ عَلَيْهَا
زَكَرِيَّا ٱلْمِحْرَابَ وَجَدَ عِندَهَا رِزْقًا ۖ قَالَ يَٰمَرْيَمُ أَنَّىٰ لَكِ هَٰذَا ۖ
قَالَتْ هُوَ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ يَرْزُقُ مَن يَشَآءُ بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴿٣٧﴾

(30) Ranar da kowane rai zai sami abin da ya aikata na alheri an halarto da shi, abin da kuwa ya aikata na mummunan aiki, zai so ina ma da a ce tsakaninsa da shi akwai wata tazara mai nisa. Kuma Allah Yana tsoratar da ku kansa, kuma Allah Mai tausayi ne ga bayi (31) Ka ce: "In kun kasance kuna son Allah, to ku yi mini biyayya, sai Allah Ya so ku, kuma Ya gafarta muku zunubanku. Kuma Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai."
(32) Ka ce: "Ku yi ɗa'a ga Allah da Manzo; to in kuwa kuka juya baya, to lalle Allah ba Ya son kafirai."

(33) Lalle Allah Ya zaɓi Adamu, da Nuhu da iyalan gidan Ibrahimu da iyalan gidan Imrana Ya fifita su a kan sauran talikai
(34) Wata zurriya ce, sashinsu 'ya'ya ne ga sashi. Kuma Allah Mai ji ne, Mai yawan sani
(35) Tuna lokacin da matar Imrana ta ce: "Ya Ubangijina, lalle ni na yi maka bakancen abin da yake cikina ya zamanto 'yantacce, don haka Ka karɓa daga gare ni, lalle Kai ne Mai ji, Mai yawan sani."
(36) To yayin da ta haife ta sai ta ce: "Ya Ubangijina, lalle ni na haife ta 'ya mace," kuma Allah ne Ya fi sanin abin da ta haifa "Kuma ɗa namiji ba daidai yake da 'ya mace ba; kuma lalle ni na raɗa mata suna Maryamu, kuma lalle ni ina nema mata tsarinka da zurriyarta daga Shaiɗan korarre."
(37) Sai Ubangijinta Ya karɓe ta da kyakkyawar karɓa, kuma Ya yi mata kyakkyawar tarbiyya, kuma Ya danƙa renonta a hannun Zakariyya; duk lokacin da Zakariyya ya shiga wurinta a ɗakin ibada, sai ya sami abinci a wurinta, sai ya ce: "Ya ke Maryamu, wannan daga ina kika samu?" Sai ta ce: "Wannan daga Allah ne; lalle Allah Yana arzurta wanda Ya ga dama ba tare da lissafi ba."

هُنَالِكَ دَعَا زَكَرِيَّا رَبَّهُۥ ۖ قَالَ رَبِّ هَبْ لِى مِن لَّدُنكَ ذُرِّيَّةً
طَيِّبَةً ۖ إِنَّكَ سَمِيعُ ٱلدُّعَآءِ ﴿٣٨﴾ فَنَادَتْهُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَهُوَ قَآئِمٌ
يُصَلِّى فِى ٱلْمِحْرَابِ أَنَّ ٱللَّهَ يُبَشِّرُكَ بِيَحْيَىٰ مُصَدِّقًۢا بِكَلِمَةٍ
مِّنَ ٱللَّهِ وَسَيِّدًا وَحَصُورًا وَنَبِيًّا مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿٣٩﴾ قَالَ رَبِّ
أَنَّىٰ يَكُونُ لِى غُلَٰمٌ وَقَدْ بَلَغَنِىَ ٱلْكِبَرُ وَٱمْرَأَتِى عَاقِرٌ ۖ قَالَ
كَذَٰلِكَ ٱللَّهُ يَفْعَلُ مَا يَشَآءُ ﴿٤٠﴾ قَالَ رَبِّ ٱجْعَل لِّىٓ ءَايَةً ۚ
قَالَ ءَايَتُكَ أَلَّا تُكَلِّمَ ٱلنَّاسَ ثَلَٰثَةَ أَيَّامٍ إِلَّا رَمْزًا ۗ وَٱذْكُر
رَّبَّكَ كَثِيرًا وَسَبِّحْ بِٱلْعَشِىِّ وَٱلْإِبْكَٰرِ ﴿٤١﴾ وَإِذْ قَالَتِ
ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَٰمَرْيَمُ إِنَّ ٱللَّهَ ٱصْطَفَىٰكِ وَطَهَّرَكِ وَٱصْطَفَىٰكِ
عَلَىٰ نِسَآءِ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٤٢﴾ يَٰمَرْيَمُ ٱقْنُتِى لِرَبِّكِ وَٱسْجُدِى
وَٱرْكَعِى مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ ﴿٤٣﴾ ذَٰلِكَ مِنْ أَنۢبَآءِ ٱلْغَيْبِ نُوحِيهِ إِلَيْكَ ۚ
وَمَا كُنتَ لَدَيْهِمْ إِذْ يُلْقُونَ أَقْلَٰمَهُمْ أَيُّهُمْ يَكْفُلُ مَرْيَمَ
وَمَا كُنتَ لَدَيْهِمْ إِذْ يَخْتَصِمُونَ ﴿٤٤﴾ إِذْ قَالَتِ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ
يَٰمَرْيَمُ إِنَّ ٱللَّهَ يُبَشِّرُكِ بِكَلِمَةٍ مِّنْهُ ٱسْمُهُ ٱلْمَسِيحُ عِيسَى
ٱبْنُ مَرْيَمَ وَجِيهًا فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ وَمِنَ ٱلْمُقَرَّبِينَ ﴿٤٥﴾

(38) A wannan lokacin sai Zakariyya ya roƙi Ubangijinsa, ya ce: "Ya Ubangijina, Ka ba ni zurriyya ta gari daga gare Ka, lalle Kai Mai amsa roƙo ne."
(39) Sai mala'iku suka kira shi, lokacin yana tsaye yana salla a cikin ɗakin ibada, (suka ce): "Lalle Allah Yana yi maka albishir da Yahya, wanda yake mai gaskatawa da wata kalma daga Allah, kuma zai zama shugaba, kuma mai tsare kansa daga mata, kuma Annabi daga cikin salihan bayi."
(40) Ya ce: "Ya Ubangijina, ta yaya zan sami ɗa, ga shi tsufa ya riga ya cim mini, kuma ga shi matata juya ce?" Sai ya ce: "Kamar haka ne Allah Yake aikata abin da Ya ga dama."
(41) Ya ce: "Ya Ubangijina, Ka sanya mini wata alama." Ya ce: "Alamarka ita ce ka kasa yi wa mutane magana yini uku sai dai da nuni. Kuma ka ambaci Ubangijinka ambato mai yawa, kuma ka yi tasbihi yammaci da safiya."
(42) Kuma ka tuna lokacin da mala'iku suka ce: "Ya ke Maryamu, lalle Allah Ya zaɓe ki, Ya kuma tsarkake ki, kuma Ya zaɓe ki a kan sauran mata na talikai
(43) "Ya ke Maryamu, ki yi ɗa'a ga Ubangijinki, kuma ki rika yin sujada, kuma ki rika yin ruku'u tare da masu ruku'u
(44) Wancan (abin da ya gabata a baya) yana cikin labaru na gaibi da Muke yi maka wahayinsa, kuma kai ba ka wurinsu lokacin da suka jefa alƙalumansu don tantance wane ne cikinsu zai karɓi renon Maryamu, kuma kai ba ka nan tare da su yayin da suke jayayya da juna
(45) Ka tuna lokacin da mala'iku suka ce: "Ya ke Maryamu, lalle Allah Yana yi miki albishir da wata kalma daga gare shi, sunansa Almasihu Isa ɗan Maryamu, mai daraja a duniya da lahira, kuma yana cikin bayi makusanta

وَيُكَلِّمُ ٱلنَّاسَ فِى ٱلْمَهْدِ وَكَهْلًا وَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿٤٦﴾
قَالَتْ رَبِّ أَنَّىٰ يَكُونُ لِى وَلَدٌ وَلَمْ يَمْسَسْنِى بَشَرٌ ۖ قَالَ كَذَٰلِكِ
ٱللَّهُ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ ۚ إِذَا قَضَىٰٓ أَمْرًا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ
﴿٤٧﴾ وَيُعَلِّمُهُ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ وَٱلتَّوْرَىٰةَ وَٱلْإِنجِيلَ
﴿٤٨﴾ وَرَسُولًا إِلَىٰ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ أَنِّى قَدْ جِئْتُكُم بِـَٔايَةٍ مِّن
رَّبِّكُمْ أَنِّىٓ أَخْلُقُ لَكُم مِّنَ ٱلطِّينِ كَهَيْـَٔةِ ٱلطَّيْرِ فَأَنفُخُ
فِيهِ فَيَكُونُ طَيْرًۢا بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۖ وَأُبْرِئُ ٱلْأَكْمَهَ وَٱلْأَبْرَصَ
وَأُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰ بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۖ وَأُنَبِّئُكُم بِمَا تَأْكُلُونَ وَمَا تَدَّخِرُونَ
فِى بُيُوتِكُمْ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَةً لَّكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٤٩﴾
وَمُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَىَّ مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ وَلِأُحِلَّ لَكُم
بَعْضَ ٱلَّذِى حُرِّمَ عَلَيْكُمْ ۚ وَجِئْتُكُم بِـَٔايَةٍ مِّن رَّبِّكُمْ
فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿٥٠﴾ إِنَّ ٱللَّهَ رَبِّى وَرَبُّكُمْ فَٱعْبُدُوهُ ۗ
هَٰذَا صِرَٰطٌ مُّسْتَقِيمٌ ﴿٥١﴾ ۞ فَلَمَّآ أَحَسَّ عِيسَىٰ مِنْهُمُ
ٱلْكُفْرَ قَالَ مَنْ أَنصَارِىٓ إِلَى ٱللَّهِ ۖ قَالَ ٱلْحَوَارِيُّونَ نَحْنُ
أَنصَارُ ٱللَّهِ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَٱشْهَدْ بِأَنَّا مُسْلِمُونَ ﴿٥٢﴾

(46) “Kuma zai rika yi wa mutane magana tun yana cikin shimfidar jego da kuma lokacin da ya zama dattijo, kuma yana cikin salihan bayi.”
(47) Sai ta ce: “Ya Ubangijina, ta yaya zan sami ɗa alhalin wani namiji bai kusance ni ba?” Sai ya ce: “Kamar haka ne Allah Yake halittar abin da Ya ga dama. Idan Ya yi zartar da wani al’amari, sai Ya ce da shi: “Kasance” Nan take sai ya kasance
(48) “Kuma zai sanar da shi rubutu da hikima da Attaura da Linjila
(49) “Kuma zai aiko shi a matsayin Manzo ga Banu Isra’ila (yana mai cewa): “Lalle ni na zo muku da wata aya daga Ubangijinku; lalle ni zan rika mulmula muku tabo a siffar tsuntsu, sai in yi busa a cikinsa sai ya zama tsuntsu da izinin Allah; kuma zan warkar da wanda aka haifa makaho da mai cutar albaras, kuma in rayar da matattu da izinin Allah; kuma zan rika ba ku labarin abin da kuke ci da abin da kuke ajiyewa a gidajenku. Lalle a cikin hakan akwai aya a gare ku in har kun kasance muminai
(50) “Kuma zan zama mai gaskata abin da ya gabace ni na Attaura, kuma don in halatta muku sashin abubuwan da aka haramta muku. Kuma na zo muku da wata aya daga Ubangijinku, don haka ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku yi mini biyayya
(51) “Lalle Allah Shi ne Ubangijina kuma Ubangijinku, don haka ku bautata masa Shi kadai. Wannan shi ne tafarki madaidaici.”
(52) To yayin da Isa ya ga alamun kafirci a tare da su sai ya ce: “Su wane ne za su taimake ni wajen kira zuwa ga Allah?” Sai Hawariyawa suka ce: “Mu ne mataimaka addinin Allah, mun yi imani da Allah, kuma ka ba da shaida cewa, mu Musulmai ne

رَبَّنَآ ءَامَنَّا بِمَآ أَنزَلْتَ وَٱتَّبَعْنَا ٱلرَّسُولَ فَٱكْتُبْنَا مَعَ
ٱلشَّٰهِدِينَ ﴿٥٣﴾ وَمَكَرُوا۟ وَمَكَرَ ٱللَّهُ ۖ وَٱللَّهُ خَيْرُ ٱلْمَٰكِرِينَ
﴿٥٤﴾ إِذْ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَىٰٓ إِنِّى مُتَوَفِّيكَ وَرَافِعُكَ إِلَىَّ وَمُطَهِّرُكَ
مِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَجَاعِلُ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوكَ فَوْقَ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوٓا۟ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ ۖ ثُمَّ إِلَىَّ مَرْجِعُكُمْ فَأَحْكُمُ
بَيْنَكُمْ فِيمَا كُنتُمْ فِيهِ تَخْتَلِفُونَ ﴿٥٥﴾ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟
فَأُعَذِّبُهُمْ عَذَابًا شَدِيدًا فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ وَمَا لَهُم
مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿٥٦﴾ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
فَيُوَفِّيهِمْ أُجُورَهُمْ ۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٥٧﴾ ذَٰلِكَ نَتْلُوهُ
عَلَيْكَ مِنَ ٱلْءَايَٰتِ وَٱلذِّكْرِ ٱلْحَكِيمِ ﴿٥٨﴾ إِنَّ مَثَلَ
عِيسَىٰ عِندَ ٱللَّهِ كَمَثَلِ ءَادَمَ ۖ خَلَقَهُۥ مِن تُرَابٍ ثُمَّ قَالَ لَهُۥ
كُن فَيَكُونُ ﴿٥٩﴾ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَلَا تَكُن مِّنَ ٱلْمُمْتَرِينَ
﴿٦٠﴾ فَمَنْ حَآجَّكَ فِيهِ مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَكَ مِنَ ٱلْعِلْمِ فَقُلْ تَعَالَوْا۟
نَدْعُ أَبْنَآءَنَا وَأَبْنَآءَكُمْ وَنِسَآءَنَا وَنِسَآءَكُمْ وَأَنفُسَنَا
وَأَنفُسَكُمْ ثُمَّ نَبْتَهِلْ فَنَجْعَل لَّعْنَتَ ٱللَّهِ عَلَى ٱلْكَٰذِبِينَ ﴿٦١﴾

(53) “Ya Ubangijinmu, mun yi imani da abin da Ka saukar, kuma mun yi ɗa’a ga Manzo, don haka Ka rubuta mu tare da masu shaida.”

(54) Sai suka shirya makirci, sai Allah Ya mayar musu da martani game da makircinsu; kuma Allah Shi ne Fiyayyen masu mayar da martanin makirci

(55) Kuma ka tuna lokacin da Allah Ya ce: “Ya kai Isa, lalle Ni Mai karɓar ranka ne, kuma Ni Mai ɗaukaka ka ne zuwa gare Ni, kuma zan tsarkake ka daga (cutarwar) waɗanda suka kafirta, kuma zan ɗora waɗanda suka bi ka a kan waɗanda suka kafirta har zuwa ranar tashin alƙiyama; sannan zuwa gare Ni ne makomarku take, sai In yi hukunci a tsakaninku game da abin da kuke saɓani a kansa

(56) Amma waɗanda suka kafirce, zan yi musu azaba mai tsanani a duniya da lahira, kuma ba su da wasu mataimaka.”

(57) Amma kuma waɗanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyuka nagari, to (Allah) zai cika musu ladansu. Kuma Allah ba Ya son azzalumai

(58) “Wannan (labarin) Muna karanta maka shi ne daga ayoyi da kuma Alkur’ani mai hikima.”

(59) Lalle misalin Isa a wurin Allah kamar misalin Adamu ne; Ya halicce shi daga turɓaya, sannan Ya ce da shi: “Kasance.” nan take sai ya kasance

(60) Gaskiya ce daga wajen Ubangijinka, don haka kar ka kasance cikin masu yin kokwanto

(61) To duk wanda ya yi jayayya da kai cikin lamarinsa (Isa) bayan abin da ya zo maka na ilimi, to ka ce: “Ku zo mu kirawo ‘ya’yanmu da ‘ya’yanku da matanmu da matanku da mu kanmu da ku kanku, sannan mu ƙasƙantar da kawunanmu cikin addu’a don mu roƙi tsinuwar Allah ta tabbata a kan maƙaryata”

إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ ٱلْقَصَصُ ٱلْحَقُّ ۚ وَمَا مِنْ إِلَٰهٍ إِلَّا ٱللَّهُ ۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهُوَ
ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٦٢﴾ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَإِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِٱلْمُفْسِدِينَ
﴿٦٣﴾ قُلْ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ تَعَالَوْا۟ إِلَىٰ كَلِمَةٍ سَوَآءٍۭ بَيْنَنَا
وَبَيْنَكُمْ أَلَّا نَعْبُدَ إِلَّا ٱللَّهَ وَلَا نُشْرِكَ بِهِۦ شَيْـًٔا وَلَا يَتَّخِذَ
بَعْضُنَا بَعْضًا أَرْبَابًا مِّن دُونِ ٱللَّهِ ۚ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَقُولُوا۟ ٱشْهَدُوا۟
بِأَنَّا مُسْلِمُونَ ﴿٦٤﴾ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ لِمَ تُحَآجُّونَ فِىٓ إِبْرَٰهِيمَ
وَمَآ أُنزِلَتِ ٱلتَّوْرَىٰةُ وَٱلْإِنجِيلُ إِلَّا مِنۢ بَعْدِهِۦٓ ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ
﴿٦٥﴾ هَٰٓأَنتُمْ هَٰٓؤُلَآءِ حَٰجَجْتُمْ فِيمَا لَكُم بِهِۦ عِلْمٌ فَلِمَ
تُحَآجُّونَ فِيمَا لَيْسَ لَكُم بِهِۦ عِلْمٌ ۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ
لَا تَعْلَمُونَ ﴿٦٦﴾ مَا كَانَ إِبْرَٰهِيمُ يَهُودِيًّا وَلَا نَصْرَانِيًّا
وَلَٰكِن كَانَ حَنِيفًا مُّسْلِمًا وَمَا كَانَ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٦٧﴾
إِنَّ أَوْلَى ٱلنَّاسِ بِإِبْرَٰهِيمَ لَلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُ وَهَٰذَا ٱلنَّبِىُّ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ ۗ وَٱللَّهُ وَلِىُّ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٦٨﴾ وَدَّت طَّآئِفَةٌ مِّنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ
لَوْ يُضِلُّونَكُمْ ۚ وَمَا يُضِلُّونَ إِلَّآ أَنفُسَهُمْ ۖ وَمَا يَشْعُرُونَ ﴿٦٩﴾ يَٰٓأَهْلَ
ٱلْكِتَٰبِ لِمَ تَكْفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَأَنتُمْ تَشْهَدُونَ ﴿٧٠﴾

(62) Lalle wannan shi ne ba da labari na gaskiya. Kuma babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah. Kuma lalle Allah Shi ne Mabuwayi, Mai hikima

(63) To idan sun ba da baya, to lalle Allah Yana sane da mafarnata

(64) Ka ce: "Ya ku Ma'abota Littafi, ku taho ga wata kalma mai daidaitawa tsakaninmu da ku cewa, kar mu bauta wa kowa sai Allah, kuma kar mu haɗa Shi da wani, kuma kada wani sashi a cikinmu ya riƙi wani sashi a matsayin abin bauta ba Allah ba." Idan kuwa sun ba da baya, to ku ce: "Ku shaida cewa, lalle mu Musulmi ne."

(65) Ya ku Ma'abota Littafi, don me kuke yin jayayya game da Ibrahimu, alhalin ba a saukar da Attaura da Linjila ba sai bayan shuɗewarsa? Yanzu ba za ku hankalta ba?

(66) Ga ku nan ku waɗannan kun yi jayayya kan abin da kuke da ilimi a kai, to don me kuma kuke jayayya a kan abin da ba ku da ilimi a kansa? Kuma Allah Yana sane ku ba ku sani ba

(67) Ibrahimu bai taɓa zama Bayahude ba, sannan bai taɓa zama Banasare ba, sai dai ya kasance mai barin ɓarna ne, Musulmi, kuma bai kasance ɗaya daga cikin mushirikai ba

(68) Lalle mafi kusancin mutane da Ibrahimu su ne waɗanda suka bi shi, sai kuma wannan Annabin, da kuma waɗanda suka yi Imani. Kuma Allah shi ne Majiɓincin al'amuran muminai

(69) Wata ƙungiya daga cikin Ma'abota Littatafi sun yi burin ina ma sun ɓatar da ku, kuma ba za su ɓatar da kowa ba sai kawunansu, amma ba sa sanin hakan

(70) Ya ku Ma'abota Littafi, don me kuke kafirce wa ayoyin Allah, alhalin ku kuna shaidawa (cewa gaskiya ne)?

يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ لِمَ تَلۡبِسُونَ ٱلۡحَقَّ بِٱلۡبَٰطِلِ وَتَكۡتُمُونَ ٱلۡحَقَّ
وَأَنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٧١ وَقَالَت طَّآئِفَةٞ مِّنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ ءَامِنُواْ
بِٱلَّذِيٓ أُنزِلَ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَجۡهَ ٱلنَّهَارِ وَٱكۡفُرُوٓاْ ءَاخِرَهُۥ
لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ٧٢ وَلَا تُؤۡمِنُوٓاْ إِلَّا لِمَن تَبِعَ دِينَكُمۡ قُلۡ إِنَّ
ٱلۡهُدَىٰ هُدَى ٱللَّهِ أَن يُؤۡتَىٰٓ أَحَدٞ مِّثۡلَ مَآ أُوتِيتُمۡ أَوۡ يُحَآجُّوكُمۡ
عِندَ رَبِّكُمۡۗ قُلۡ إِنَّ ٱلۡفَضۡلَ بِيَدِ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ
وَٰسِعٌ عَلِيمٞ ٧٣ يَخۡتَصُّ بِرَحۡمَتِهِۦ مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ
ٱلۡعَظِيمِ ٧٤ ۞ وَمِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ مَنۡ إِن تَأۡمَنۡهُ بِقِنطَارٖ
يُؤَدِّهِۦٓ إِلَيۡكَ وَمِنۡهُم مَّنۡ إِن تَأۡمَنۡهُ بِدِينَارٖ لَّا يُؤَدِّهِۦٓ إِلَيۡكَ
إِلَّا مَا دُمۡتَ عَلَيۡهِ قَآئِمٗاۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَالُواْ لَيۡسَ عَلَيۡنَا فِي
ٱلۡأُمِّيِّـۧنَ سَبِيلٞ وَيَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ
٧٥ بَلَىٰ مَنۡ أَوۡفَىٰ بِعَهۡدِهِۦ وَٱتَّقَىٰ فَإِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُتَّقِينَ
٧٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَشۡتَرُونَ بِعَهۡدِ ٱللَّهِ وَأَيۡمَٰنِهِمۡ ثَمَنٗا قَلِيلًا
أُوْلَٰٓئِكَ لَا خَلَٰقَ لَهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ وَلَا يُكَلِّمُهُمُ ٱللَّهُ وَلَا يَنظُرُ
إِلَيۡهِمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَلَا يُزَكِّيهِمۡ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٧٧

(71) Ya ku Ma'abota Littafi, don me kuke cakuɗa gaskiya da ƙarya, kuma kuke ɓoye gaskiya, alhalin ku kuna sane?
(72) Kuma wata ƙungiya cikin Ma'abota Littafi suka ce: "Ku yi imani mana da abin da aka saukar wa waɗanda suka yi imani a farkon yini, kuma ku kafirce a ƙarshen yini, mai yiwuwa ne su dawo (daga rakiyar addininsu) (73) "Kuma kada ku amince da kowa sai wanda ya bi addininku." Ka ce: "Lalle shiriya ita ce shiriyar Allah, domin kar (ku yarda a ce) an ba wani mutum irin abin da aka ba ku, ko kuma ku ba su dama su yi jayayya da ku a wajen Ubangijinku." Ka ce: "Lalle falala a hannun Allah take, Yana bayar da ita ga wanda Ya ga dama. Kuma Allah Mai yalwa ne, Mai yawan sani
(74) "Yana keɓantar wanda Ya ga dama da rahamarsa, kuma Allah Ma'abocin falala ne wadda take mai girma."
(75) Kuma daga cikin Ma'abota Littafi akwai wanda in da za ka ba shi amana ta dukiya mai yawa, zai dawo maka da ita, daga cikinsu kuwa akwai wanda idan da za ka ba shi amana ta dinare ɗaya, ba zai dawo maka da shi ba, sai fa idan ka tashi tsaye a kansa. Wannan kuwa saboda sun ce: "Babu wani laifi a kanmu (don mun ci dukiyar) bobayin mutane." Kuma suna faɗin ƙarya su jingina wa Allah, alhalin su suna sane
(76) Ba haka ba ne, duk wanda ya cika alƙawarinsa, kuma ya tsare dokar Allah, to lalle Allah Yana son masu taƙawa
(77) Lalle waɗanda suke musanya alƙawarin Allah da rantse-rantsensu da wani ɗan farashi ƙanƙani, waɗannan ba su da wani rabo a lahira, kuma Allah ba zai yi musu magana ba, kuma ba zai dube su (duba na rahama) ba a ranar alƙiyama, kuma ba zai tsarkake su ba, kuma suna da azaba mai raɗaɗi

وَإِنَّ مِنْهُمْ لَفَرِيقًا يَلْوُۥنَ أَلْسِنَتَهُم بِٱلْكِتَٰبِ لِتَحْسَبُوهُ
مِنَ ٱلْكِتَٰبِ وَمَا هُوَ مِنَ ٱلْكِتَٰبِ وَيَقُولُونَ هُوَ مِنْ
عِندِ ٱللَّهِ وَمَا هُوَ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ وَيَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ
وَهُمْ يَعْلَمُونَ ﴿٧٨﴾ مَا كَانَ لِبَشَرٍ أَن يُؤْتِيَهُ ٱللَّهُ ٱلْكِتَٰبَ
وَٱلْحُكْمَ وَٱلنُّبُوَّةَ ثُمَّ يَقُولَ لِلنَّاسِ كُونُوا۟ عِبَادًا لِّى مِن
دُونِ ٱللَّهِ وَلَٰكِن كُونُوا۟ رَبَّٰنِيِّۧنَ بِمَا كُنتُمْ تُعَلِّمُونَ
ٱلْكِتَٰبَ وَبِمَا كُنتُمْ تَدْرُسُونَ ﴿٧٩﴾ وَلَا يَأْمُرَكُمْ أَن
تَتَّخِذُوا۟ ٱلْمَلَٰٓئِكَةَ وَٱلنَّبِيِّۧنَ أَرْبَابًا ۚ أَيَأْمُرُكُم بِٱلْكُفْرِ بَعْدَ
إِذْ أَنتُم مُّسْلِمُونَ ﴿٨٠﴾ وَإِذْ أَخَذَ ٱللَّهُ مِيثَٰقَ ٱلنَّبِيِّۧنَ لَمَآ ءَاتَيْتُكُم
مِّن كِتَٰبٍ وَحِكْمَةٍ ثُمَّ جَآءَكُمْ رَسُولٌ مُّصَدِّقٌ لِّمَا
مَعَكُمْ لَتُؤْمِنُنَّ بِهِۦ وَلَتَنصُرُنَّهُۥ ۚ قَالَ ءَأَقْرَرْتُمْ وَأَخَذْتُمْ
عَلَىٰ ذَٰلِكُمْ إِصْرِى ۖ قَالُوٓا۟ أَقْرَرْنَا ۚ قَالَ فَٱشْهَدُوا۟ وَأَنَا۠ مَعَكُم
مِّنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ﴿٨١﴾ فَمَن تَوَلَّىٰ بَعْدَ ذَٰلِكَ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ
ٱلْفَٰسِقُونَ ﴿٨٢﴾ أَفَغَيْرَ دِينِ ٱللَّهِ يَبْغُونَ وَلَهُۥٓ أَسْلَمَ مَن فِى
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ طَوْعًا وَكَرْهًا وَإِلَيْهِ يُرْجَعُونَ ﴿٨٣﴾

(78) Kuma lalle daga cikinsu akwai wani ɓangare da suke karkatar da harshensu lokacin karanta Littafin (Attaura), don ku yi zaton yana cikin Littafin, alhali kuwa ba ya cikin Littafin, kuma za su rika cewa, shi (wahayi ne saukakke) daga wurin Allah, alhalin kuwa ba daga wurin Allah yake ba, kuma za su rika faɗar ƙarya suna jingina wa Allah, alhalin suna sane

(79) Bai dace ba ga wani mutum wanda Allah zai ba shi littafi da hukunci da annabci, sannan ya ce wa mutane: "Ku zama bayina ba na Allah ba," sai dai (ya ce): "Ku zamo malamai na Allah saboda abin da kuke karantarwa na littafi, kuma saboda abin da kuka kasance kuna karantawa."

(80) Kuma ba zai umarce ku da ku riki mala'iku ko annabawa a matsayin iyayengiji ba; yanzu zai umarce ku da kafirci ne bayan kuna Musulmi?

(81) Kuma ka tuna lokacin da Allah Ya yi alƙawari da annabawa cewa: "Duk irin abin da Na ba ku na littafi da wata hikima, sannan sai wani Manzo ya zo muku mai gaskata abin da yake tare da ku, to lalle ku yi imani da shi, kuma lalle ku taimake shi." Ya ce: "Shin kun yarda da hakan, kuma kun ɗauki alƙawarina a kan hakan?" Suka ce: "Mun yarda da haka." Ya ce: "To ku shaida, kuma Ni ma Ina tare da ku cikin masu shaidawa."

(82) To duk wanda ya juya baya bayan wannan, to waɗannan su ne fasiƙai

(83) To shin yanzu wani addini suke nema ba na Allah ba, alhalin duk wanda yake cikin sammai da ƙasa gare Shi ne ya miƙa wuya yana so ko yana ƙi, kuma zuwa gare Shi za a komar da su?

قُلْ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ عَلَيْنَا وَمَآ أُنزِلَ عَلَىٰٓ إِبْرَٰهِيمَ
وَإِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ وَٱلْأَسْبَاطِ وَمَآ أُوتِيَ مُوسَىٰ
وَعِيسَىٰ وَٱلنَّبِيُّونَ مِن رَّبِّهِمْ لَا نُفَرِّقُ بَيْنَ أَحَدٍ مِّنْهُمْ
وَنَحْنُ لَهُۥ مُسْلِمُونَ ﴿٨٤﴾ وَمَن يَبْتَغِ غَيْرَ ٱلْإِسْلَٰمِ دِينًا فَلَن
يُقْبَلَ مِنْهُ وَهُوَ فِى ٱلْءَاخِرَةِ مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿٨٥﴾ كَيْفَ
يَهْدِى ٱللَّهُ قَوْمًا كَفَرُوا۟ بَعْدَ إِيمَٰنِهِمْ وَشَهِدُوٓا۟ أَنَّ
ٱلرَّسُولَ حَقٌّ وَجَآءَهُمُ ٱلْبَيِّنَٰتُ ۚ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ
ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٨٦﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ جَزَآؤُهُمْ أَنَّ عَلَيْهِمْ لَعْنَةَ ٱللَّهِ
وَٱلْمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلنَّاسِ أَجْمَعِينَ ﴿٨٧﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَا لَا يُخَفَّفُ
عَنْهُمُ ٱلْعَذَابُ وَلَا هُمْ يُنظَرُونَ ﴿٨٨﴾ إِلَّا ٱلَّذِينَ تَابُوا۟ مِنۢ
بَعْدِ ذَٰلِكَ وَأَصْلَحُوا۟ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٨٩﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ بَعْدَ إِيمَٰنِهِمْ ثُمَّ ٱزْدَادُوا۟ كُفْرًا لَّن تُقْبَلَ تَوْبَتُهُمْ
وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلضَّآلُّونَ ﴿٩٠﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَمَاتُوا۟ وَهُمْ
كُفَّارٌ فَلَن يُقْبَلَ مِنْ أَحَدِهِم مِّلْءُ ٱلْأَرْضِ ذَهَبًا وَلَوِ
ٱفْتَدَىٰ بِهِۦٓ ۗ أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿٩١﴾

(84) Ka ce: “Mun yi imani da Allah da abin da aka saukar mana da kuma abin da aka saukar wa Ibrahim da Isma’ila da Ishaƙ da Ya’aƙub da jikokin (Ya’aƙub), da abin da aka ba wa Musa da Isa da abin da aka ba wa annabawa daga Ubangijinsu; ba ma nuna bambanci a kan ɗaya daga cikinsu, kuma mu muna masu miƙa wuya gare Shi.”

(85) Duk kuma wanda ya nemi (bin) wani addini ba Musulunci ba, to har abada ba za a karɓa daga gare shi ba, kuma shi a lahira yana cikin hasararru

(86) Ta yaya Allah zai shiryar da mutanen da suka kafirta bayan imaninsu, kuma bayan sun shaida cewa, Manzon gaskiya ne, kuma hujjoji sun zo musu? Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane azzalumai

(87) Waɗannan sakamakonsu (shi ne), lalle la’antar Allah za ta tabbata a kansu da ta mala’iku da mutane gaba ɗaya

(88) Suna masu dawwama a cikinta, ba za a sassauta musu azaba ba, kuma ba za a jinkirta musu ba

(89) Sai fa waɗanda suka sake tuba bayan haka, kuma suka gyara (ayyukansu), to lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(90) Lalle waɗanda suka kafirta bayan imaninsu, sannan suka ƙara zurfi cikin kafirci, to ba za a karɓi tubansu ba, kuma waɗannan su ne ɓatattu

(91) Lalle waɗanda suka kafirta, kuma suka mutu alhali suna kafirai, to ba za a taɓa karɓar cikin ƙasa na zinare daga ɗayansu ba, ko da zai fanshi kansa da shi. Waɗannan suna da wata azaba mai raɗaɗi kuma ba su da wasu mataimaka

لَن تَنَالُوا۟ ٱلْبِرَّ حَتَّىٰ تُنفِقُوا۟ مِمَّا تُحِبُّونَ ۚ وَمَا تُنفِقُوا۟ مِن شَىْءٍ
فَإِنَّ ٱللَّهَ بِهِۦ عَلِيمٌ ﴿٩٢﴾ ۞ كُلُّ ٱلطَّعَامِ كَانَ حِلًّا لِّبَنِىٓ
إِسْرَٰٓءِيلَ إِلَّا مَا حَرَّمَ إِسْرَٰٓءِيلُ عَلَىٰ نَفْسِهِۦ مِن قَبْلِ أَن تُنَزَّلَ
ٱلتَّوْرَىٰةُ ۗ قُلْ فَأْتُوا۟ بِٱلتَّوْرَىٰةِ فَٱتْلُوهَآ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ
﴿٩٣﴾ فَمَنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ مِنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ فَأُو۟لَٰٓئِكَ
هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٩٤﴾ قُلْ صَدَقَ ٱللَّهُ ۗ فَٱتَّبِعُوا۟ مِلَّةَ إِبْرَٰهِيمَ حَنِيفًا
وَمَا كَانَ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٩٥﴾ إِنَّ أَوَّلَ بَيْتٍ وُضِعَ لِلنَّاسِ لَلَّذِى
بِبَكَّةَ مُبَارَكًا وَهُدًى لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿٩٦﴾ فِيهِ ءَايَٰتٌۢ بَيِّنَٰتٌ مَّقَامُ
إِبْرَٰهِيمَ ۖ وَمَن دَخَلَهُۥ كَانَ ءَامِنًا ۗ وَلِلَّهِ عَلَى ٱلنَّاسِ حِجُّ ٱلْبَيْتِ
مَنِ ٱسْتَطَاعَ إِلَيْهِ سَبِيلًا ۚ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَنِىٌّ عَنِ ٱلْعَٰلَمِينَ
﴿٩٧﴾ قُلْ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ لِمَ تَكْفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَٱللَّهُ شَهِيدٌ
عَلَىٰ مَا تَعْمَلُونَ ﴿٩٨﴾ قُلْ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ لِمَ تَصُدُّونَ عَن
سَبِيلِ ٱللَّهِ مَنْ ءَامَنَ تَبْغُونَهَا عِوَجًا وَأَنتُمْ شُهَدَآءُ ۗ وَمَا ٱللَّهُ
بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿٩٩﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِن تُطِيعُوا۟ فَرِيقًا
مِّنَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ يَرُدُّوكُم بَعْدَ إِيمَٰنِكُمْ كَٰفِرِينَ ﴿١٠٠﴾

(92) Ba za ku taɓa dacewa da aiki na alheri ba har sai kun ciyar daga abin da kuke so, kuma abin da duk kuka ciyar kowane iri ne, to lalle Allah Yana sane da shi

(93) Duk wani abinci ya kasance halal ne ga Banu Israila sai abin da shi Isra'ilu[1] ya haramta wa kansa tun kafin a saukar da Attaura. Ka ce: "To ku zo da Attaura, sai ku karanta ta in kun kasance masu gaskiya."

(94) To duk wanda ya ƙirƙiri ƙarya ya jingina wa Allah bayan wannan, to waɗannan su ne azzalumai

(95) Ka ce: "Allah Ya yi gaskiya. Don haka ku bi addinin Ibrahimu, mai karkace wa ɓarna, kuma bai taɓa zama ɗaya daga cikin mushirikai ba."

(96) Lalle farkon ɗaki da aka tanada don mutane (su yi ibada a cikinsa) shi ne wanda yake cikin Bakka[2] (ɗaki ne) mai albarka, kuma shiriya ne ga talikai

(97) A cikinsa akwai ayoyi bayyanannu, (kuma akwai) Maƙamu Ibrahimu; wanda duk ya shige shi ya zama amintacce. Kuma Allah Ya wajabta wa mutane ziyarar wannan ɗakin ga wanda ya sami iko[3]. Wanda kuwa ya kafirce, to lalle Allah Mawadaci ne ga barin talikai

(98) Ka ce: "Ya ku Ma'abota Littafi, don me kuke kafirce wa ayoyin Allah, kuma alhalin Allah Mai ba da shaida ne ga abin da kuke aikatawa?"

(99) Ka ce: "Ya ku Ma'abota Littafi, don me kuke kange wanda ya yi imani daga hanyar Allah, kuna son ta zamo karkatacciya, kuma alhali ku da kanku masu shaida ne, kuma Allah ba gafalalle ne game da abin da kuke aikatawa ba?"

(100) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka bi wani ɓangare na waɗanda aka ba wa Littafi, to za su mayar da ku kafirai bayan imaninku

(1) Isra'ilu: shi ne Annabi Ya'aƙub ( ). Ya haramta wa kansa ne cin naman raƙuma da shan nononsu. Sannan daga baya su ma 'ya'yansa suka yi koyi da shi.

(2) Watau Ɗakin Ka'aba da yake garin Makka mai alfarma.

(3) Allah ya farlanta ziyarar wannan Ɗaki domin aikin hajji sau ɗaya a rayuwa ga duk wanda ya sami iko na lafiya da guzuri da abin hawa da amincin hanya.

وَكَيْفَ تَكْفُرُونَ وَأَنتُمْ تُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ ءَايَٰتُ ٱللَّهِ وَفِيكُمْ
رَسُولُهُۥ ۗ وَمَن يَعْتَصِم بِٱللَّهِ فَقَدْ هُدِىَ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿١٠١﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ حَقَّ تُقَاتِهِۦ وَلَا تَمُوتُنَّ إِلَّا وَأَنتُم
مُّسْلِمُونَ ﴿١٠٢﴾ وَٱعْتَصِمُوا۟ بِحَبْلِ ٱللَّهِ جَمِيعًا وَلَا تَفَرَّقُوا۟ ۚ وَٱذْكُرُوا۟
نِعْمَتَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ إِذْ كُنتُمْ أَعْدَآءً فَأَلَّفَ بَيْنَ قُلُوبِكُمْ
فَأَصْبَحْتُم بِنِعْمَتِهِۦٓ إِخْوَٰنًا وَكُنتُمْ عَلَىٰ شَفَا حُفْرَةٍ مِّنَ
ٱلنَّارِ فَأَنقَذَكُم مِّنْهَا ۗ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمْ ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمْ
تَهْتَدُونَ ﴿١٠٣﴾ وَلْتَكُن مِّنكُمْ أُمَّةٌ يَدْعُونَ إِلَى ٱلْخَيْرِ وَيَأْمُرُونَ
بِٱلْمَعْرُوفِ وَيَنْهَوْنَ عَنِ ٱلْمُنكَرِ ۚ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ﴿١٠٤﴾
وَلَا تَكُونُوا۟ كَٱلَّذِينَ تَفَرَّقُوا۟ وَٱخْتَلَفُوا۟ مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلْبَيِّنَٰتُ ۚ
وَأُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿١٠٥﴾ يَوْمَ تَبْيَضُّ وُجُوهٌ وَتَسْوَدُّ
وُجُوهٌ ۚ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ٱسْوَدَّتْ وُجُوهُهُمْ أَكَفَرْتُم بَعْدَ إِيمَٰنِكُمْ
فَذُوقُوا۟ ٱلْعَذَابَ بِمَا كُنتُمْ تَكْفُرُونَ ﴿١٠٦﴾ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ ٱبْيَضَّتْ
وُجُوهُهُمْ فَفِى رَحْمَةِ ٱللَّهِ ۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿١٠٧﴾ تِلْكَ ءَايَٰتُ
ٱللَّهِ نَتْلُوهَا عَلَيْكَ بِٱلْحَقِّ ۗ وَمَا ٱللَّهُ يُرِيدُ ظُلْمًا لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿١٠٨﴾

(101) Ta yaya kuma za ku kafirce, ga shi kuwa ana karanta muku ayoyin Allah, kuma Manzonsa yana tare da ku? Duk kuwa wanda ya riƙi Allah, to haƙiƙa an shiryar da shi tafarki madaidaici

(102) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi taƙawa ga Allah haƙiƙanin taƙawa, kuma lalle kada ku mutu face kuna Musulmi

(103) Kuma ku yi riƙo da igiyar Allah gaba ɗaya, kada kuma ku rarraba. Kuma ku tuna ni'imar Allah da Ya yi muku yayin da kuka zamo abokan gaban juna sai Ya haɗa tsakanin zukatanku, sai kuka zamo 'yan'uwan juna a sakamakon ni'imarsa, a da kuma kun kasance a kan gaɓar ramin wuta sai Ya tserar da ku daga gare ta. Kamar haka ne Allah Yake bayyana muku ayoyinsa don ku shiriya

(104) A cikinku lalle a sami wata al'umma waɗanda suke kira zuwa ga alheri, kuma suke umarni da kyakkyawa, kuma suke hana mummuna. Waɗannan su ne masu rabauta

(105) Kuma kada ku kasance kamar waɗanda suka rarrabu, kuma suka sassaɓa bayan hujjoji sun zo musu. Waɗannan kuwa suna da azaba mai girma

(106) Ranar da waɗansu fuskoki za su yi fari, waɗansu fuskokin kuma za su yi baƙi. Amma waɗanda fuskokinsu suka yi baƙi, (za a ce da su): "Shin ku ne kuka kafirce bayan imaninku? To ku ɗanɗani azaba, saboda kafircin da kuka kasance kuna yi."

(107) Amma waɗanda fuskokinsu suka yi fari kuwa, to suna cikin rahamar Allah, suna masu dawwama a cikinta

(108) Waɗannan ayoyin Allah ne Muke karanta maka su da gaskiya. Kuma Allah ba Ya nufin zalunci ga talikai

وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرۡجَعُ ٱلۡأُمُورُ
﴿١٠٩﴾ كُنتُمۡ خَيۡرَ أُمَّةٍ أُخۡرِجَتۡ لِلنَّاسِ تَأۡمُرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ
وَتَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَتُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِۗ وَلَوۡ ءَامَنَ أَهۡلُ
ٱلۡكِتَٰبِ لَكَانَ خَيۡرٗا لَّهُمۚ مِّنۡهُمُ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ وَأَكۡثَرُهُمُ
ٱلۡفَٰسِقُونَ ﴿١١٠﴾ لَن يَضُرُّوكُمۡ إِلَّآ أَذٗىۖ وَإِن يُقَٰتِلُوكُمۡ
يُوَلُّوكُمُ ٱلۡأَدۡبَارَ ثُمَّ لَا يُنصَرُونَ ﴿١١١﴾ ضُرِبَتۡ عَلَيۡهِمُ
ٱلذِّلَّةُ أَيۡنَ مَا ثُقِفُوٓاْ إِلَّا بِحَبۡلٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَحَبۡلٖ مِّنَ ٱلنَّاسِ
وَبَآءُو بِغَضَبٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَضُرِبَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلۡمَسۡكَنَةُۚ ذَٰلِكَ
بِأَنَّهُمۡ كَانُواْ يَكۡفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَيَقۡتُلُونَ ٱلۡأَنۢبِيَآءَ
بِغَيۡرِ حَقّٖۚ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَواْ وَّكَانُواْ يَعۡتَدُونَ ﴿١١٢﴾ * لَيۡسُواْ
سَوَآءٗۗ مِّنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ أُمَّةٞ قَآئِمَةٞ يَتۡلُونَ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ
ءَانَآءَ ٱلَّيۡلِ وَهُمۡ يَسۡجُدُونَ ﴿١١٣﴾ يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ
ٱلۡأٓخِرِ وَيَأۡمُرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ
وَيُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿١١٤﴾ وَمَا
يَفۡعَلُواْ مِنۡ خَيۡرٖ فَلَن يُكۡفَرُوهُۗ وَٱللَّهُ عَلِيمُۢ بِٱلۡمُتَّقِينَ ﴿١١٥﴾

(109) Kuma duk abin da yake cikin sammai da ƙasa na Allah ne. Kuma zuwa ga Allah ne ake mayar da duk al'amura

(110) Ku ne mafi alherin al'umma wadanda aka fitar ga mutane, kuna umarni da kyakkyawan aiki, kuma kuna hana mummuna, kuma kuna yin imani da Allah. Da a ce kuwa Ma'abota Littafi za su yi imani da ya fi alheri a gare su. A cikinsu akwai muminai, amma mafiya yawansu fasiƙai ne

(111) Ba za su taɓa iya cutar da ku ba sai dai cutarwa kaɗan; kuma in da za su yaƙe ku, sai sun juya muku baya, sannan ba za a taimake su ba

(112) An haɗa su da ƙasƙanci a duk inda aka same su, sai dai wadanda suke riƙe da wani alƙawari daga Allah ko wani alƙawari daga mutane, kuma sun dawo da wani fushi daga Allah, kuma an haɗa su da talauci. Hakan kuwa saboda sun kasance suna kafirce wa ayoyin Allah, kuma suna kashe annabawa ba tare da wani haƙƙi ba, hakan yana faruwa ne saboda saɓo da suka yi, kuma sun kasance suna ƙetare iyaka

(113) Ba dukansu ne suka zama ɗaya ba. Cikin Ma'abota Littafi akwai al'umma tsayayya, suna karanta Littafin Allah a cikin dare alhalin suna sujada

(114) Suna yin imani da Allah da ranar ƙarshe, kuma suna umarni da kyakkyawan aiki, kuma suna hana mummuna, kuma suna hanzari wajen ayyukan alheri, waɗannan kuwa suna cikin salihan bayi

(115) Kuma duk abin da suka aikata na alheri, to ba za a hana musu ladansa ba. Kuma Allah Yana sane da masu taƙawa

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَن تُغۡنِيَ عَنۡهُمۡ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُم مِّنَ
ٱللَّهِ شَيۡـٔٗاۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ١١٦
مَثَلُ مَا يُنفِقُونَ فِي هَٰذِهِ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا كَمَثَلِ رِيحٖ فِيهَا
صِرٌّ أَصَابَتۡ حَرۡثَ قَوۡمٖ ظَلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ فَأَهۡلَكَتۡهُۚ وَمَا
ظَلَمَهُمُ ٱللَّهُ وَلَٰكِنۡ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ١١٧ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ بِطَانَةٗ مِّن دُونِكُمۡ لَا يَأۡلُونَكُمۡ خَبَالٗا
وَدُّواْ مَا عَنِتُّمۡ قَدۡ بَدَتِ ٱلۡبَغۡضَآءُ مِنۡ أَفۡوَٰهِهِمۡ وَمَا تُخۡفِي
صُدُورُهُمۡ أَكۡبَرُۚ قَدۡ بَيَّنَّا لَكُمُ ٱلۡأٓيَٰتِۖ إِن كُنتُمۡ تَعۡقِلُونَ
١١٨ هَٰٓأَنتُمۡ أُوْلَآءِ تُحِبُّونَهُمۡ وَلَا يُحِبُّونَكُمۡ وَتُؤۡمِنُونَ بِٱلۡكِتَٰبِ
كُلِّهِۦ وَإِذَا لَقُوكُمۡ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا وَإِذَا خَلَوۡاْ عَضُّواْ عَلَيۡكُمُ
ٱلۡأَنَامِلَ مِنَ ٱلۡغَيۡظِۚ قُلۡ مُوتُواْ بِغَيۡظِكُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمُۢ بِذَاتِ
ٱلصُّدُورِ ١١٩ إِن تَمۡسَسۡكُمۡ حَسَنَةٞ تَسُؤۡهُمۡ وَإِن تُصِبۡكُمۡ
سَيِّئَةٞ يَفۡرَحُواْ بِهَاۖ وَإِن تَصۡبِرُواْ وَتَتَّقُواْ لَا يَضُرُّكُمۡ كَيۡدُهُمۡ
شَيۡـًٔاۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِمَا يَعۡمَلُونَ مُحِيطٞ ١٢٠ وَإِذۡ غَدَوۡتَ مِنۡ أَهۡلِكَ
تُبَوِّئُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ مَقَٰعِدَ لِلۡقِتَالِۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ١٢١

(116) Lalle waɗanda suka kafirta, dukiyoyinsu da ‘ya’yansu ba za su wadatar da su komai ba a wurin Allah; kuma waɗannan su ne ma’abota wuta; suna masu dawwama a cikinta

(117) Misalin abin da suke ciyarwa a wannan rayuwa ta duniya kamar misalin iska ce mai tsananin sanyi, wadda ta auka kan shukar waɗansu mutanen da suka zalunci kawunansu, sai ta lalata ta. Kuma Allah bai zalunce su ba, sai dai kawunansu suke zalunta

(118) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku riƙi abokanan shawara waɗanda ba a cikinku suke ba, ba za su sassauta muku mugunta ba, sun yi burin duk abin da zai ƙuntata muku, haƙiƙa ƙiyayya ta bayyana daga bakunansu; amma abin da zukatansu suke ɓoyewa ya fi girma. Haƙiƙa Mun bayyana muku ayoyi; in kun kasance kuna hankalta

(119) Sai ga shi ku ɗinnan kuna son su, su kuwa ba sa son ku, kuma ku kuna yin imani da Littattafai gaba ɗayansu, kuma idan sun gamu da ku, sai su ce: “Mun yi imani.” Idan kuma sun keɓanta, sai su riƙa cizon ‘yan yatsu a kanku saboda baƙin ciki. Ka ce: “Sai dai ku mutu da baƙin cikinku.” Lalle Allah Masanin abin da yake cikin ƙiraza ne

(120) Idan wani kyakkyawan abu ya same ku sai ya baƙanta musu rai, amma idan wani mummunan abu ya same ku, sai su riƙa farin ciki da shi; amma idan kuwa kuka yi haƙuri, kuma kuka yi taƙawa, makircinsu ba zai cutar da ku komai ba. Lalle Allah Yana kewaye da sanin abin da suke aikatawa

(121) Kuma ka tuna lokacin da ka yi sammako daga wajen iyalinka, ka je kana shirya wa muminai wuraren tsayuwarsu don yaƙi[1]. Allah kuwa Mai ji ne, Masani

(1) Watau lokacin fitarsa zuwa yaƙin Uhudu shekara ta uku bayan hijira.

إِذْ هَمَّت طَّآئِفَتَانِ مِنكُمْ أَن تَفْشَلَا وَٱللَّهُ وَلِيُّهُمَا ۗ وَعَلَى ٱللَّهِ
فَلْيَتَوَكَّلِ ٱلْمُؤْمِنُونَ ﴿١٢٢﴾ وَلَقَدْ نَصَرَكُمُ ٱللَّهُ بِبَدْرٍ وَأَنتُمْ أَذِلَّةٌ ۖ
فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿١٢٣﴾ إِذْ تَقُولُ لِلْمُؤْمِنِينَ
أَلَن يَكْفِيَكُمْ أَن يُمِدَّكُمْ رَبُّكُم بِثَلَٰثَةِ ءَالَٰفٍ مِّنَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ
مُنزَلِينَ ﴿١٢٤﴾ بَلَىٰٓ إِن تَصْبِرُوا۟ وَتَتَّقُوا۟ وَيَأْتُوكُم مِّن فَوْرِهِمْ
هَٰذَا يُمْدِدْكُمْ رَبُّكُم بِخَمْسَةِ ءَالَٰفٍ مِّنَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ مُسَوِّمِينَ
﴿١٢٥﴾ وَمَا جَعَلَهُ ٱللَّهُ إِلَّا بُشْرَىٰ لَكُمْ وَلِتَطْمَئِنَّ قُلُوبُكُم بِهِۦ ۚ
وَمَا ٱلنَّصْرُ إِلَّا مِنْ عِندِ ٱللَّهِ ٱلْعَزِيزِ ٱلْحَكِيمِ ﴿١٢٦﴾ لِيَقْطَعَ طَرَفًا
مِّنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ أَوْ يَكْبِتَهُمْ فَيَنقَلِبُوا۟ خَآئِبِينَ ﴿١٢٧﴾
لَيْسَ لَكَ مِنَ ٱلْأَمْرِ شَىْءٌ أَوْ يَتُوبَ عَلَيْهِمْ أَوْ يُعَذِّبَهُمْ فَإِنَّهُمْ
ظَٰلِمُونَ ﴿١٢٨﴾ وَلِلَّهِ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۚ يَغْفِرُ لِمَن
يَشَآءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ ۗ وَٱللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٢٩﴾ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَأْكُلُوا۟ ٱلرِّبَوٰٓا۟ أَضْعَٰفًا مُّضَٰعَفَةً ۖ
وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿١٣٠﴾ وَٱتَّقُوا۟ ٱلنَّارَ ٱلَّتِىٓ أُعِدَّتْ
لِلْكَٰفِرِينَ ﴿١٣١﴾ وَأَطِيعُوا۟ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿١٣٢﴾

(122) Tuna lokacin da waɗansu ƙungiyoyi guda biyu daga cikinku suka yi niyyar su ja da baya[1], amma Allah ne Majiɓincin lamarinsu. Sai muminai su dogara ga Allah kaɗai

(123) Kuma tabbas haƙiƙa Allah Ya taimake ku a (yaƙin) Badar, alhalin kuna raunana, to ku ji tsoron Allah don ku zamanto masu godiya a gare Shi

(124) Ka tuna lokacin da kake ce wa muminai: “Shin bai ishe ku ba idan Ubangijinku Ya kawo muku agajin mala’iku dubu uku waɗanda za a saukar da su (daga sama)?”

(125) Haka ne, idan har za ku yi haƙuri, kuma ku yi taƙawa, kuma (kafirai) suka auko muku cikin gaggawa a wannan lokacin, to Ubangijinku zai ƙaro muku agaji da mala’iku dubu biyar masu alamomi

(126) Kuma Allah bai sanya wannan ba sai don albishir a gare ku, kuma domin zukatanku su nutsu da shi. Kuma nasara ba ta zuwa daga kowa sai daga Allah Mabuwayi, Mai hikima

(127) Domin Ya karya lagon wani ɓangare na kafirai ko Ya ƙasƙantar da su, sai su juya da baya suna taɓaɓɓu

(128) Ba ka da komai cikin lamarin, ko dai (Allah) Ya karɓi tubansu, ko Ya yi musu azaba, lalle su dai azzalumai ne

(129) Kuma abin da yake cikin sammai da kuma abin da yake cikin ƙasa na Allah ne. Yana yin gafara ga wanda Ya ga dama, Yana kuma yin azaba ga wanda Ya ga dama. Kuma Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(130) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ci riba ninki-ba-ninkin, kuma ku kiyaye dokokin Allah don ku rabauta

(131) Kuma ku kiyayi wuta wadda aka riga aka yi tanadinta domin kafirai

(132) Kuma ku bi Allah da Manzo don a ji ƙan ku (a ranar tashin alƙiyama)

(1) Kungiyoyin muminai biyu da suka yi nufin su janye daga wannan yaƙi, su ne ƙabilun Banu Salima da na Banu Harisa, sai dai kuma Allah ya kafe dugadugansu.



وَسَارِعُوٓاْ إِلَىٰ مَغۡفِرَةٖ مِّن رَّبِّكُمۡ وَجَنَّةٍ عَرۡضُهَا
ٱلسَّمَٰوَٰتُ وَٱلۡأَرۡضُ أُعِدَّتۡ لِلۡمُتَّقِينَ ١٣٣ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ
فِي ٱلسَّرَّآءِ وَٱلضَّرَّآءِ وَٱلۡكَٰظِمِينَ ٱلۡغَيۡظَ وَٱلۡعَافِينَ
عَنِ ٱلنَّاسِۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٣٤ وَٱلَّذِينَ إِذَا فَعَلُواْ
فَٰحِشَةً أَوۡ ظَلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ ذَكَرُواْ ٱللَّهَ فَٱسۡتَغۡفَرُواْ
لِذُنُوبِهِمۡ وَمَن يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ إِلَّا ٱللَّهُ وَلَمۡ يُصِرُّواْ عَلَىٰ مَا
فَعَلُواْ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ١٣٥ أُوْلَٰٓئِكَ جَزَآؤُهُم مَّغۡفِرَةٞ مِّن
رَّبِّهِمۡ وَجَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ وَنِعۡمَ
أَجۡرُ ٱلۡعَٰمِلِينَ ١٣٦ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِكُمۡ سُنَنٞ فَسِيرُواْ
فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ
١٣٧ هَٰذَا بَيَانٞ لِّلنَّاسِ وَهُدٗى وَمَوۡعِظَةٞ لِّلۡمُتَّقِينَ ١٣٨
وَلَا تَهِنُواْ وَلَا تَحۡزَنُواْ وَأَنتُمُ ٱلۡأَعۡلَوۡنَ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ
١٣٩ إِن يَمۡسَسۡكُمۡ قَرۡحٞ فَقَدۡ مَسَّ ٱلۡقَوۡمَ قَرۡحٞ مِّثۡلُهُۥۚ وَتِلۡكَ
ٱلۡأَيَّامُ نُدَاوِلُهَا بَيۡنَ ٱلنَّاسِ وَلِيَعۡلَمَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
وَيَتَّخِذَ مِنكُمۡ شُهَدَآءَۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٤٠

Lorem ipsum

(133) Kuma ku yi gaggawa zuwa ga neman gafara ta musamman daga wajen Ubangijinku, da kuma Aljanna wadda fadinta yake daidai da sammai da kasa, an yi tanadinta domin masu takawa

(134) (Su ne) wadanda suke ciyarwa a cikin halin yalwa da halin kunci, kuma masu boye fushi kuma masu yin afuwa ga mutane. Allah kuwa Yana son masu kyautatawa

(135) (Su ne) kuma wadanda idan sun aikata mummunan aiki, ko suka zalunci kansu, nan take sai su tuna da Allah, sai su nemi gafarar zunubansu. Wane ne kuwa mai gafarta zunubbai in ba Allah ba? Kuma ba sa zarcewa a kan abin da suka yi, alhali suna sane

(136) Wadannan sakamakonsu shi ne gafara ta musamman daga Ubangijinsu, da gidajen Aljanna wadanda koramu suke gudana ta karkashinsu, suna masu dawwama a cikinsu. Kuma madalla da sakamakon masu aiki

(137) Hakika sunnoni (na Allah) sun riga sun shude gabaninku, to sai ku yi tafiya cikin kasa, sai ku duba ku ga yaya karshen masu karyatawa ya zama?

(138) Wannan bayani ne don mutane, kuma shiriya ce da kuma wa'azi ga masu takawa

(139) Kuma kada ku yi rauni, kada kuma ku yi bakin ciki, kuma ku ne mafiya daukaka in dai har kun kasance muminai

(140) Idan ma wani miki ne ya same ku a jiki, to hakika miki irinsa ya sami mutanen (Makka). Kuma wadannan kwanaki ne da muke jujjuya su tsakanin mutane domin Allah Ya bayyanar da wadanda suka yi imani (a gane su), kuma Ya riki shahidai a cikinku. Allah kuwa ba Ya son azzalumai

وَلِيُمَحِّصَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَيَمۡحَقَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ﴿١٤١﴾ أَمۡ
حَسِبۡتُمۡ أَن تَدۡخُلُواْ ٱلۡجَنَّةَ وَلَمَّا يَعۡلَمِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ جَٰهَدُواْ
مِنكُمۡ وَيَعۡلَمَ ٱلصَّٰبِرِينَ ﴿١٤٢﴾ وَلَقَدۡ كُنتُمۡ تَمَنَّوۡنَ ٱلۡمَوۡتَ مِن
قَبۡلِ أَن تَلۡقَوۡهُ فَقَدۡ رَأَيۡتُمُوهُ وَأَنتُمۡ تَنظُرُونَ ﴿١٤٣﴾ وَمَا مُحَمَّدٌ
إِلَّا رَسُولٞ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِهِ ٱلرُّسُلُۚ أَفَإِي۟ن مَّاتَ أَوۡ قُتِلَ
ٱنقَلَبۡتُمۡ عَلَىٰٓ أَعۡقَٰبِكُمۡۚ وَمَن يَنقَلِبۡ عَلَىٰ عَقِبَيۡهِ فَلَن يَضُرَّ
ٱللَّهَ شَيۡـٔٗاۗ وَسَيَجۡزِي ٱللَّهُ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿١٤٤﴾ وَمَا كَانَ
لِنَفۡسٍ أَن تَمُوتَ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِ كِتَٰبٗا مُّؤَجَّلٗاۗ وَمَن يُرِدۡ
ثَوَابَ ٱلدُّنۡيَا نُؤۡتِهِۦ مِنۡهَا وَمَن يُرِدۡ ثَوَابَ ٱلۡأٓخِرَةِ نُؤۡتِهِۦ مِنۡهَاۚ
وَسَنَجۡزِي ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿١٤٥﴾ وَكَأَيِّن مِّن نَّبِيّٖ قَٰتَلَ مَعَهُۥ
رِبِّيُّونَ كَثِيرٞۖ فَمَا وَهَنُواْ لِمَآ أَصَابَهُمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَمَا ضَعُفُواْ
وَمَا ٱسۡتَكَانُواْۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلصَّٰبِرِينَ ﴿١٤٦﴾ وَمَا كَانَ قَوۡلَهُمۡ إِلَّآ أَن
قَالُواْ رَبَّنَا ٱغۡفِرۡ لَنَا ذُنُوبَنَا وَإِسۡرَافَنَا فِيٓ أَمۡرِنَا وَثَبِّتۡ أَقۡدَامَنَا
وَٱنصُرۡنَا عَلَى ٱلۡقَوۡمِ ٱلۡكَٰفِرِينَ ﴿١٤٧﴾ فَـَٔاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ ثَوَابَ
ٱلدُّنۡيَا وَحُسۡنَ ثَوَابِ ٱلۡأٓخِرَةِۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ﴿١٤٨﴾

(141) Kuma don Allah Ya tace waɗanda suka yi imani, kuma don Ya halakar da kafirai
(142) Yanzu kuna tsammanin za ku shiga Aljanna ne alhalin Allah bai bayyanar da masu yin jihadi daga cikinku ba, kuma bai bayyanar da masu haƙuri ba
(143) Kuma haƙiƙa kun kasance a da can kuna ta burin mutuwa tun kafin ku gamu da ita, to haƙiƙa (a yau) ga ta kun gan ta alhali kuna kallo da ido
(144) Kuma Muhammadu ba wani ne ba face Manzo kaɗai wanda manzanni haƙiƙa sun shuɗe gabaninsa. Shin yanzu idan ya mutu ko aka kashe shi, sai ku juya baya a kan dugaduganku? Duk kuwa wanda ya juya baya a kan dugadugansa to ba zai cuci Allah da komai ba. Kuma da sannu Allah zai saka wa masu godiya
(145) Kuma babu wani rai da zai mutu sai da izinin Allah, rubutaccen abu ne ƙayyadajje. Kuma duk wanda yake nufin sakamakon duniya, za Mu ba shi daga gare ta, wanda kuma yake nufin sakamakon lahira, to za Mu ba shi daga gare ta. Kuma da sannu za Mu saka ma masu godiya
(146) Kuma sau da yawa an sami wani annabi (daga cikin annabawa), mabiya masu yawa sun yi yaƙi tare da shi, amma ba su taɓa yin rauni ba saboda abin da ya same su a tafarkin Allah, kuma ba su taɓa yin ragwanci ba, kuma ba su taɓa miƙa wuya ba. Kuma Allah Yana son masu haƙuri
(147) Kuma ba su da wata magana sai faɗar: "Ya Ubangijinmu, Ka gafarta mana zunubanmu da ƙetare iyakar da muka yi cikin lamurranmu, kuma Ka tabbatar da dugaduganmu, kuma Ka taimake mu a kan mutunen da suke kafirai
(148) Sai Allah Ya ba su ladan duniya da kyakkyawan lada na lahira. Kuma Allah Yana son masu kyautatawa

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن تُطِيعُواْ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
يَرُدُّوكُمۡ عَلَىٰٓ أَعۡقَٰبِكُمۡ فَتَنقَلِبُواْ خَٰسِرِينَ
﴿١٤٩﴾ بَلِ ٱللَّهُ مَوۡلَىٰكُمۡۖ وَهُوَ خَيۡرُ ٱلنَّٰصِرِينَ ﴿١٥٠﴾ سَنُلۡقِي
فِي قُلُوبِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلرُّعۡبَ بِمَآ أَشۡرَكُواْ بِٱللَّهِ
مَا لَمۡ يُنَزِّلۡ بِهِۦ سُلۡطَٰنٗاۖ وَمَأۡوَىٰهُمُ ٱلنَّارُۖ وَبِئۡسَ
مَثۡوَى ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٥١﴾ وَلَقَدۡ صَدَقَكُمُ ٱللَّهُ
وَعۡدَهُۥٓ إِذۡ تَحُسُّونَهُم بِإِذۡنِهِۦۖ حَتَّىٰٓ إِذَا فَشِلۡتُمۡ
وَتَنَٰزَعۡتُمۡ فِي ٱلۡأَمۡرِ وَعَصَيۡتُم مِّنۢ بَعۡدِ مَآ أَرَىٰكُم
مَّا تُحِبُّونَۚ مِنكُم مَّن يُرِيدُ ٱلدُّنۡيَا وَمِنكُم مَّن
يُرِيدُ ٱلۡأٓخِرَةَۚ ثُمَّ صَرَفَكُمۡ عَنۡهُمۡ لِيَبۡتَلِيَكُمۡۖ
وَلَقَدۡ عَفَا عَنكُمۡۗ وَٱللَّهُ ذُو فَضۡلٍ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ
﴿١٥٢﴾ ۞ إِذۡ تُصۡعِدُونَ وَلَا تَلۡوُۥنَ عَلَىٰٓ أَحَدٖ
وَٱلرَّسُولُ يَدۡعُوكُمۡ فِيٓ أُخۡرَىٰكُمۡ فَأَثَٰبَكُمۡ
غَمَّۢا بِغَمّٖ لِّكَيۡلَا تَحۡزَنُواْ عَلَىٰ مَا فَاتَكُمۡ وَلَا
مَآ أَصَابَكُمۡۗ وَٱللَّهُ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ﴿١٥٣﴾

(149) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan har kuka yi biyayya ga waɗanda suka kafirta, to za su mayar da ku baya a kan dugaduganku, sai ku juya kuna hasararru

(150) A'a, Allah Shi ne Majiɓincin lamarinku; kuma Shi ne Fiyayyen masu taimako

(151) Da sannu za Mu jefa tsoro a cikin zukatan waɗanda suka kafirta saboda abin da suka yi na sanya wa Allah kishiya, abin da bai saukar da hujja a kai ba; kuma makomarsu ita ce wuta. Kuma tir da makomar azzalumai (idan ta zama wuta)

(152) Kuma tabbas haƙiƙa Allah Ya cika muku alƙawarinsa yayin da kuka rifka kisan su da yawa da izininsa; har zuwa lokacin da kuka yi rauni, kuma kuka yi jayayya a cikin umarnin (Manzo), kuma daga ƙarshe kuka saɓa bayan (Allah) Ya nuna muku irin abin da kuke so. Cikinku akwai waɗanda suke nufin duniya, kuma cikinku akwai waɗanda suke nufin lahira. Sannan sai Ya kautar da ku kuka bar su don ya jarrabe ku; kuma tabbas haƙiƙa Allah Ya yi muku afuwa. Kuma Allah Ma'abocin falala ne ga muminai

(153) Ka tuna lokacin da kuke guduwa ba kwa waiwaye ma ku ga wanda yake baya da ku, kuma Manzo yana can bayanku yana ta kiran ku, sai (Allah) Ya saka muku da damuwa bisa damuwa domin kar ku yi baƙin ciki a kan abin da ya kuɓuce muku, da abin da ya same ku. Allah kuma Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne

ثُمَّ أَنزَلَ عَلَيْكُم مِّنۢ بَعْدِ ٱلْغَمِّ أَمَنَةً نُّعَاسًا يَغْشَىٰ طَآئِفَةً
مِّنكُمْ ۖ وَطَآئِفَةٌ قَدْ أَهَمَّتْهُمْ أَنفُسُهُمْ يَظُنُّونَ بِٱللَّهِ غَيْرَ
ٱلْحَقِّ ظَنَّ ٱلْجَٰهِلِيَّةِ ۖ يَقُولُونَ هَل لَّنَا مِنَ ٱلْأَمْرِ مِن شَىْءٍ ۗ
قُلْ إِنَّ ٱلْأَمْرَ كُلَّهُۥ لِلَّهِ ۗ يُخْفُونَ فِىٓ أَنفُسِهِم مَّا لَا يُبْدُونَ لَكَ ۖ
يَقُولُونَ لَوْ كَانَ لَنَا مِنَ ٱلْأَمْرِ شَىْءٌ مَّا قُتِلْنَا هَٰهُنَا ۗ قُل لَّوْ كُنتُمْ
فِى بُيُوتِكُمْ لَبَرَزَ ٱلَّذِينَ كُتِبَ عَلَيْهِمُ ٱلْقَتْلُ إِلَىٰ مَضَاجِعِهِمْ ۖ
وَلِيَبْتَلِىَ ٱللَّهُ مَا فِى صُدُورِكُمْ وَلِيُمَحِّصَ مَا فِى قُلُوبِكُمْ ۗ
وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿١٥٤﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَوَلَّوْا۟ مِنكُمْ
يَوْمَ ٱلْتَقَى ٱلْجَمْعَانِ إِنَّمَا ٱسْتَزَلَّهُمُ ٱلشَّيْطَٰنُ بِبَعْضِ
مَا كَسَبُوا۟ ۖ وَلَقَدْ عَفَا ٱللَّهُ عَنْهُمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ حَلِيمٌ ﴿١٥٥﴾ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَكُونُوا۟ كَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَقَالُوا۟ لِإِخْوَٰنِهِمْ إِذَا
ضَرَبُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ أَوْ كَانُوا۟ غُزًّى لَّوْ كَانُوا۟ عِندَنَا مَا مَاتُوا۟
وَمَا قُتِلُوا۟ لِيَجْعَلَ ٱللَّهُ ذَٰلِكَ حَسْرَةً فِى قُلُوبِهِمْ ۗ وَٱللَّهُ يُحْىِۦ
وَيُمِيتُ ۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿١٥٦﴾ وَلَئِن قُتِلْتُمْ فِى سَبِيلِ
ٱللَّهِ أَوْ مُتُّمْ لَمَغْفِرَةٌ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَحْمَةٌ خَيْرٌ مِّمَّا يَجْمَعُونَ ﴿١٥٧﴾

(154) Sannan bayan damuwa sai (Allah) Ya saukar muku da kwanciyar hankali har gyangyadi yana ɗaukar wasu daga cikinku; amma wani sashin kuma tasu ta ishe su, suna yi wa Allah zato wanda ba na gaskiya ba, zato irin na jahiliyya; suna cewa: “Anya kuwa muna da ta cewa cikin wannan lamari?” Ka ce: “Lalle al’amari gaba ɗaya na Allah ne.” Suna ɓoyewa a cikin rayukansu abin da ba sa bayyana maka shi; suna cewa: “In da al’amarin a hannunmu yake ai da ba a kashe mu a nan ba.” Ka ce: “Ko da kun kasance kuna cikin gidajenku, tabbas da waɗanda aka rubuta za su mutu sun fito da kansu, sun zo inda nan ne za su kwanta (dama).” Kuma Allah (Ya ɗaukaka haka) don Ya jarraba abin da yake cikin ɓirazanku, kuma don Ya tace abin da yake cikin zukatanku. Kuma Allah Masanin abin da yake cikin ɓiraza ne

(155) Lalle waɗanda suka gudu daga cikinku yayin da runduna biyu suka haɗu, Shaiɗan ne ya nemi ya zamar da su saboda wani laifi da suka yi; kuma tabbas haƙiƙa Allah Ya yi musu afuwa. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai haƙuri

(156) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku kasance kamar waɗanda suka kafirta, kuma suka riɓa faɗa wa ‘yan’uwansu yayin da suka yi tafiya a bayan ɓasa, ko kuma suka kasance mayaƙa: “In da sun kasance tare da mu, ai da ba su mutu ba, kuma da ba a kashe su ba,” don Allah Ya sanya waccan (maganar) ta zamo nadama a cikin zukatansu. Kuma Allah Shi ne Mai rayawa, kuma Shi ne Mai kashewa. Kuma Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne

(157) Kuma lalle idan ma har an kashe ku a hanyar Allah ko kuma kuka mutu, to kuna da gafara ta musamman a wajen Allah da kuma rahama, wanda shi ne mafi alheri fiye da abin da suke tarawa

وَلَئِن مُّتُّمْ أَوْ قُتِلْتُمْ لَإِلَى ٱللَّهِ تُحْشَرُونَ ﴿١٥٨﴾ فَبِمَا رَحْمَةٍ مِّنَ ٱللَّهِ
لِنتَ لَهُمْ ۖ وَلَوْ كُنتَ فَظًّا غَلِيظَ ٱلْقَلْبِ لَٱنفَضُّوا۟ مِنْ حَوْلِكَ ۖ
فَٱعْفُ عَنْهُمْ وَٱسْتَغْفِرْ لَهُمْ وَشَاوِرْهُمْ فِى ٱلْأَمْرِ ۖ فَإِذَا عَزَمْتَ
فَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُتَوَكِّلِينَ ﴿١٥٩﴾ إِن يَنصُرْكُمُ ٱللَّهُ
فَلَا غَالِبَ لَكُمْ ۖ وَإِن يَخْذُلْكُمْ فَمَن ذَا ٱلَّذِى يَنصُرُكُم مِّنۢ
بَعْدِهِۦ ۗ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ ٱلْمُؤْمِنُونَ ﴿١٦٠﴾ وَمَا كَانَ لِنَبِىٍّ أَن
يَغُلَّ ۚ وَمَن يَغْلُلْ يَأْتِ بِمَا غَلَّ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۚ ثُمَّ تُوَفَّىٰ كُلُّ
نَفْسٍ مَّا كَسَبَتْ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿١٦١﴾ أَفَمَنِ ٱتَّبَعَ رِضْوَٰنَ
ٱللَّهِ كَمَنۢ بَآءَ بِسَخَطٍ مِّنَ ٱللَّهِ وَمَأْوَىٰهُ جَهَنَّمُ ۖ وَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ
﴿١٦٢﴾ هُمْ دَرَجَٰتٌ عِندَ ٱللَّهِ ۗ وَٱللَّهُ بَصِيرٌۢ بِمَا يَعْمَلُونَ ﴿١٦٣﴾ لَقَدْ
مَنَّ ٱللَّهُ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ إِذْ بَعَثَ فِيهِمْ رَسُولًا مِّنْ أَنفُسِهِمْ
يَتْلُوا۟ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتِهِۦ وَيُزَكِّيهِمْ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلْكِتَٰبَ
وَٱلْحِكْمَةَ وَإِن كَانُوا۟ مِن قَبْلُ لَفِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿١٦٤﴾ أَوَلَمَّآ
أَصَٰبَتْكُم مُّصِيبَةٌ قَدْ أَصَبْتُم مِّثْلَيْهَا قُلْتُمْ أَنَّىٰ هَٰذَا ۖ
قُلْ هُوَ مِنْ عِندِ أَنفُسِكُمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿١٦٥﴾

(158) Kuma lalle in kuka mutu ko aka kashe ku, lalle zuwa ga Allah dai za a tattara ku
(159) To saboda rahama ta musamman daga Allah, sai ka zamo mai tausasawa gare su; in da kuwa ka kasance mai kaushin mu'amala, mai ƙekasasshiyar zuciya ne, to da sun watse sun bar ka. To ka yi musu afuwa, kuma ka nema musu gafara, kuma ka nemi shawararsu cikin duk lamura; amma idan ka riga ka ƙulla niyya, to ka dogara ga Allah. Lalle Allah Yana son masu dogara a gare Shi
(160) Idan Allah Ya ba ku nasara, to ba wanda ya isa ya rinjaye ku, amma idan Ya ƭabar da ku, to wane ne ya isa ya taimake ku in ba shi ba? Kuma muminai wajibi ne su dogara ga Allah Shi kaɗai
(161) Kuma bai dace ba ga wani annabi ya yi ha'inci. Duk wanda ya yi ha'inci kuwa zai zo da abin da ya ha'inta ranar tashin alƙiyama. Sannan kowane rai a cika masa (sakamakon) abin da ya aikata, kuma su (halitta) ba za a zalunce su ba
(162) Shin yanzu wanda ya bi yardar Allah, zai yi kamar wanda ya dawo da fushin Allah, kuma makomarsa ta zamo Jahannama? Kuma tir da wannan makoma
(163) Su darajoji ne a wajen Allah. Allah kuma Mai ganin abin da suke aikatawa ne
(164) Lalle haƙiƙa Allah Ya yi baiwa ga muminai yayin da Ya aiko musu Manzo daga cikinsu, wanda yake karanta musu ayoyinsa, kuma yake tsarkake su, kuma yake koyar da su Littafi da Hikima, lalle kuma sun kasance kafin (zuwansa) tabbas suna cikin ƭata mabayyani
(165) Shin yayin da wata musifa ta same ku, wadda kuma haƙiƙa kun yi wa (kafirai) irinta ninki biyu, sai ku riƙa cewa: "Yaya haka ta faru?" Ka ce: "Ai wannan daga gare ku ne." Lalle Allah Mai iko ne a kan komai

وَمَآ أَصَـٰبَكُمْ يَوْمَ ٱلْتَقَى ٱلْجَمْعَانِ فَبِإِذْنِ ٱللَّهِ وَلِيَعْلَمَ ٱلْمُؤْمِنِينَ
١٦٦ وَلِيَعْلَمَ ٱلَّذِينَ نَافَقُوا۟ ۚ وَقِيلَ لَهُمْ تَعَالَوْا۟ قَـٰتِلُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ
أَوِ ٱدْفَعُوا۟ ۖ قَالُوا۟ لَوْ نَعْلَمُ قِتَالًا لَّا ٱتَّبَعْنَـٰكُمْ ۗ هُمْ لِلْكُفْرِ يَوْمَئِذٍ
أَقْرَبُ مِنْهُمْ لِلْإِيمَـٰنِ ۚ يَقُولُونَ بِأَفْوَٰهِهِم مَّا لَيْسَ فِى قُلُوبِهِمْ ۚ
وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا يَكْتُمُونَ ١٦٧ ٱلَّذِينَ قَالُوا۟ لِإِخْوَٰنِهِمْ وَقَعَدُوا۟
لَوْ أَطَاعُونَا مَا قُتِلُوا۟ ۗ قُلْ فَٱدْرَءُوا۟ عَنْ أَنفُسِكُمُ ٱلْمَوْتَ إِن
كُنتُمْ صَـٰدِقِينَ ١٦٨ وَلَا تَحْسَبَنَّ ٱلَّذِينَ قُتِلُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ
أَمْوَٰتًۢا ۚ بَلْ أَحْيَآءٌ عِندَ رَبِّهِمْ يُرْزَقُونَ ١٦٩ فَرِحِينَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمُ
ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ وَيَسْتَبْشِرُونَ بِٱلَّذِينَ لَمْ يَلْحَقُوا۟ بِهِم
مِّنْ خَلْفِهِمْ أَلَّا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ١٧٠ ۞ يَسْتَبْشِرُونَ
بِنِعْمَةٍ مِّنَ ٱللَّهِ وَفَضْلٍ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجْرَ
ٱلْمُؤْمِنِينَ ١٧١ ٱلَّذِينَ ٱسْتَجَابُوا۟ لِلَّهِ وَٱلرَّسُولِ مِنۢ بَعْدِ مَآ أَصَابَهُمُ
ٱلْقَرْحُ ۚ لِلَّذِينَ أَحْسَنُوا۟ مِنْهُمْ وَٱتَّقَوْا۟ أَجْرٌ عَظِيمٌ ١٧٢
ٱلَّذِينَ قَالَ لَهُمُ ٱلنَّاسُ إِنَّ ٱلنَّاسَ قَدْ جَمَعُوا۟ لَكُمْ فَٱخْشَوْهُمْ
فَزَادَهُمْ إِيمَـٰنًا وَقَالُوا۟ حَسْبُنَا ٱللَّهُ وَنِعْمَ ٱلْوَكِيلُ ١٧٣

(166) Kuma abin da ya same ku ranar da ƙungiyoyin nan biyu suka haɗu, to da izinin Allah ne, kuma don Ya bayyana muminai

(167) Kuma don Ya bayyana waɗanda suka yi munafunci; kuma aka riƙa cewa da su: “Ku zo ku yi yaƙi don Allah ko don kariya.” Sai suka ce: “Da mun san za a yi yaƙi ai da lalle mun biyo ku.” Su a wannan lokacin sun fi kusanci ga kafirci fiye da imani, suna faɗi da bakunansu abin da ba ya cikin zukatansu. Kuma Allah Ya san abin da suke ɓoyewa

(168) Su ne waɗanda suka faɗa wa ‘yan’uwansu, alhalin suna zaune a gida cewa: “In da sun bi (shawarar) mu da ba a kashe su ba.” Ka ce: “To ku kare kanku daga mutuwa in har kun kasance masu gaskiya.”

(169) Kuma kada ka yi tsammanin waɗanda aka kashe su a wajen yaɗa kalmar Allah matattu ne. A’a, rayayyu ne a wajen Ubangijinsu, ana arzurta su

(170) Suna cike da farin cikin abin da Allah Ya ba su na falalarsa, kuma suna masu yin albishir ga waɗanda ba su riga sun riske su ba daga bayansu cewa, babu jin tsoro a gare su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba

(171) Suna ta farin ciki da ni’ima daga Allah da falala, kuma Allah ba Ya tozarta ladan masu imani

(172) Waɗanda suka amsa kiran Allah da Manzo bayan miki ya same su a jikinsu(1). Lalle waɗanda suka kyautata a cikinsu, kuma suka yi taƙawa, suna da lada mai girma

(173) Su ne waɗanda mutane suka ce da su: “Lalle mutanen (Makka) fa sun tara muku runduna, to sai ku tsorace su.” Amma sai hakan ya ƙara musu imani, sai suka riƙa cewa: “Allah Ya wadace mu, kuma madalla da abin dogara (idan har Shi ne Allah).”

(1) Bayan dawowa daga yaƙin Uhudu, Annabi ( ) ya nemi sahabbai da su koma don su tunkari kafirai da aka samu labarin za su sake dawo wa Madina yaƙarsa. Aka fita har da masu raunuka a jikinsu.

فَٱنقَلَبُواْ بِنِعۡمَةٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَفَضۡلٖ لَّمۡ يَمۡسَسۡهُمۡ سُوٓءٞ وَٱتَّبَعُواْ
رِضۡوَٰنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ ذُو فَضۡلٍ عَظِيمٍ ١٧٤ إِنَّمَا ذَٰلِكُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ
يُخَوِّفُ أَوۡلِيَآءَهُۥ فَلَا تَخَافُوهُمۡ وَخَافُونِ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ١٧٥
وَلَا يَحۡزُنكَ ٱلَّذِينَ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡكُفۡرِۚ إِنَّهُمۡ لَن يَضُرُّواْ ٱللَّهَ
شَيۡـٔٗاۗ يُرِيدُ ٱللَّهُ أَلَّا يَجۡعَلَ لَهُمۡ حَظّٗا فِي ٱلۡأٓخِرَةِۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ
عَظِيمٌ ١٧٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱشۡتَرَوُاْ ٱلۡكُفۡرَ بِٱلۡإِيمَٰنِ لَن يَضُرُّواْ ٱللَّهَ
شَيۡـٔٗاۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ١٧٧ وَلَا يَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَنَّمَا
نُمۡلِي لَهُمۡ خَيۡرٞ لِّأَنفُسِهِمۡۚ إِنَّمَا نُمۡلِي لَهُمۡ لِيَزۡدَادُوٓاْ إِثۡمٗاۚ وَلَهُمۡ
عَذَابٞ مُّهِينٞ ١٧٨ مَّا كَانَ ٱللَّهُ لِيَذَرَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ عَلَىٰ مَآ أَنتُمۡ
عَلَيۡهِ حَتَّىٰ يَمِيزَ ٱلۡخَبِيثَ مِنَ ٱلطَّيِّبِۗ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُطۡلِعَكُمۡ
عَلَى ٱلۡغَيۡبِ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَجۡتَبِي مِن رُّسُلِهِۦ مَن يَشَآءُۖ فَـَٔامِنُواْ بِٱللَّهِ
وَرُسُلِهِۦۚ وَإِن تُؤۡمِنُواْ وَتَتَّقُواْ فَلَكُمۡ أَجۡرٌ عَظِيمٞ ١٧٩ وَلَا يَحۡسَبَنَّ
ٱلَّذِينَ يَبۡخَلُونَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦ هُوَ خَيۡرٗا لَّهُمۖ
بَلۡ هُوَ شَرّٞ لَّهُمۡۖ سَيُطَوَّقُونَ مَا بَخِلُواْ بِهِۦ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ وَلِلَّهِ
مِيرَٰثُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ١٨٠

(174) (A sakamakon haka) sai suka dawo da ni'ima ta musamman daga Allah da falala, wani abin ƙi bai shafe su ba, kuma (suka dace da cewa) sun bi yardar Allah. Allah kuma Ma'abocin falala ne wadda take mai girma

(175) Wannan (labarin), Shaiɗan ne kawai yake tsoratar da ku masoyansa, don haka kar ku ji tsoron su, amma ku ji tsoro Na in dai har ku muminai ne

(176) Kuma kada waɗanda suke gaggawar shiga cikin (ayyukan) kafirci, su fusata ka. Haƙiƙa su ba za su cutar da Allah komai ba. Allah Ya yi nufin ba zai sanya musu wani rabo a lahira ba; kuma suna da azaba mai girma

(177) Lalle waɗanda suka musanya imani da kafirci ba za su cutar da Allah da komai ba, kuma suna da azaba mai raɗaɗi

(178) Kuma waɗanda suka kafirta kar su yi tsammanin cewa, jinkiri da Muke yi musu wani alheri ne ga kawunansu. Ai Muna saurara musu ne kawai don su ƙara laifi (a kan laifinsu). Kuma suna da azaba mai wulaƙantarwa

(179) Da ɗai Allah ba zai ƙyale muminai a yadda kuke ɗin nan ba har sai Ya rarrabe tsakanin lalatacce da kyakkyawa. Kuma Allah ba zai sanar da ku gaibu ba, sai dai Allah Yana zaɓar wanda Ya so cikin manzanninsa ne; don haka ku yi imani da Allah da manzanninsa. Idan kun yi imani, kun yi taƙawa kuwa, to kuna da lada mai girma

(180) Kuma waɗanda suke yin rowar abin da Allah Ya ba su na falalarsa kar su yi tsammanin hakan alheri ne a gare su; a'a, hakan sharri ne a gare su; da sannu za a yi musu saƙandami da abin da suka yi rowa da shi a ranar alƙiyama. Kuma Allah Shi ne Mai gadon sammai da ƙasa. Kuma Allah Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne

لَّقَدْ سَمِعَ ٱللَّهُ قَوْلَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ فَقِيرٌ وَنَحْنُ أَغْنِيَآءُ ۘ
سَنَكْتُبُ مَا قَالُواْ وَقَتْلَهُمُ ٱلْأَنۢبِيَآءَ بِغَيْرِ حَقٍّ وَنَقُولُ
ذُوقُواْ عَذَابَ ٱلْحَرِيقِ ﴿١٨١﴾ ذَٰلِكَ بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيكُمْ
وَأَنَّ ٱللَّهَ لَيْسَ بِظَلَّٰمٍ لِّلْعَبِيدِ ﴿١٨٢﴾ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ
عَهِدَ إِلَيْنَآ أَلَّا نُؤْمِنَ لِرَسُولٍ حَتَّىٰ يَأْتِيَنَا بِقُرْبَانٍ
تَأْكُلُهُ ٱلنَّارُ ۗ قُلْ قَدْ جَآءَكُمْ رُسُلٌ مِّن قَبْلِى بِٱلْبَيِّنَٰتِ
وَبِٱلَّذِى قُلْتُمْ فَلِمَ قَتَلْتُمُوهُمْ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ
﴿١٨٣﴾ فَإِن كَذَّبُوكَ فَقَدْ كُذِّبَ رُسُلٌ مِّن قَبْلِكَ جَآءُو
بِٱلْبَيِّنَٰتِ وَٱلزُّبُرِ وَٱلْكِتَٰبِ ٱلْمُنِيرِ ﴿١٨٤﴾ كُلُّ نَفْسٍ
ذَآئِقَةُ ٱلْمَوْتِ ۗ وَإِنَّمَا تُوَفَّوْنَ أُجُورَكُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۖ
فَمَن زُحْزِحَ عَنِ ٱلنَّارِ وَأُدْخِلَ ٱلْجَنَّةَ فَقَدْ فَازَ ۗ وَمَا
ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَآ إِلَّا مَتَٰعُ ٱلْغُرُورِ ﴿١٨٥﴾ ۞ لَتُبْلَوُنَّ فِىٓ
أَمْوَٰلِكُمْ وَأَنفُسِكُمْ وَلَتَسْمَعُنَّ مِنَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ
ٱلْكِتَٰبَ مِن قَبْلِكُمْ وَمِنَ ٱلَّذِينَ أَشْرَكُوٓاْ أَذًى كَثِيرًا ۚ
وَإِن تَصْبِرُواْ وَتَتَّقُواْ فَإِنَّ ذَٰلِكَ مِنْ عَزْمِ ٱلْأُمُورِ ﴿١٨٦﴾

(181) Tabbas hakika Allah ya ji maganar wadannan da suka ce: “Lalle Allah mataulaci ne, mu ne mawadata.” Da sannu za Mu rubuta abin da suka fada, da kuma kisan da suka rika yi wa annabawa ba tare da wani hakki ba, kuma za Mu ce: “Ku dandani azaba mai kuna

(182) “Wannan kuwa, saboda abin da hannayenku suka gabatar ne, kuma lalle Allah ba mai zaluntar bayinsa ne ba.”

(183) Su ne wadanda suka ce: “Lalle Allah Ya yi alkawari da mu kar mu yi imani da kowane manzo har sai ya zo mana da wata sadaka wadda wuta za ta cinye ta.” Ka ce: “Hakika manzanni sun zo muku tun kafin ni, da hujjoji da kuma abin da kuka ce din, to don me kuka kashe su in kun kasance masu gaskiya?”

(184) To idan sun karyata ka, to hakika an karyata manzanni kafinka, wadanda suka zo da hujjoji da littattafai da Littafi mai haskakawa

(185) Kowane rai zai dandani mutuwa. Kuma a ranar alkiyama ne za a cika muku ladan ayyukanku; to duk wanda aka nisanta shi daga wuta, kuma aka shigar da shi Aljanna, to hakika ya rabauta. Kuma rayuwar duniya ba komai ba ce face jin dadi mai rudarwa

(186) Lalle za a jarrabe ku a cikin dukiyoyinku da rayukanku, kuma lalle za ku rika jin cutarwa mai yawa daga wadanda aka bai wa Littafi kafinku, haka kuma daga wadanda suke mushirikai. Amma idan har kuka yi hakuri, kuma kuka tsare dokar Allah, to lalle wannan yana daga cikin manyan al’amura

وَإِذْ أَخَذَ ٱللَّهُ مِيثَٰقَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ لَتُبَيِّنُنَّهُۥ لِلنَّاسِ
وَلَا تَكْتُمُونَهُۥ فَنَبَذُوهُ وَرَآءَ ظُهُورِهِمْ وَٱشْتَرَوْا۟ بِهِۦ ثَمَنًا
قَلِيلًا ۖ فَبِئْسَ مَا يَشْتَرُونَ ﴿١٨٧﴾ لَا تَحْسَبَنَّ ٱلَّذِينَ يَفْرَحُونَ بِمَآ
أَتَوا۟ وَّيُحِبُّونَ أَن يُحْمَدُوا۟ بِمَا لَمْ يَفْعَلُوا۟ فَلَا تَحْسَبَنَّهُم
بِمَفَازَةٍ مِّنَ ٱلْعَذَابِ ۖ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿١٨٨﴾ وَلِلَّهِ مُلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿١٨٩﴾ إِنَّ فِى
خَلْقِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَٱخْتِلَٰفِ ٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ لَءَايَٰتٍ
لِّأُو۟لِى ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿١٩٠﴾ ٱلَّذِينَ يَذْكُرُونَ ٱللَّهَ قِيَٰمًا وَقُعُودًا
وَعَلَىٰ جُنُوبِهِمْ وَيَتَفَكَّرُونَ فِى خَلْقِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ
رَبَّنَا مَا خَلَقْتَ هَٰذَا بَٰطِلًا سُبْحَٰنَكَ فَقِنَا عَذَابَ ٱلنَّارِ ﴿١٩١﴾
رَبَّنَآ إِنَّكَ مَن تُدْخِلِ ٱلنَّارَ فَقَدْ أَخْزَيْتَهُۥ ۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنْ
أَنصَارٍ ﴿١٩٢﴾ رَّبَّنَآ إِنَّنَا سَمِعْنَا مُنَادِيًا يُنَادِى لِلْإِيمَٰنِ أَنْ
ءَامِنُوا۟ بِرَبِّكُمْ فَـَٔامَنَّا ۚ رَبَّنَا فَٱغْفِرْ لَنَا ذُنُوبَنَا وَكَفِّرْ عَنَّا
سَيِّـَٔاتِنَا وَتَوَفَّنَا مَعَ ٱلْأَبْرَارِ ﴿١٩٣﴾ رَبَّنَا وَءَاتِنَا مَا وَعَدتَّنَا عَلَىٰ
رُسُلِكَ وَلَا تُخْزِنَا يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۗ إِنَّكَ لَا تُخْلِفُ ٱلْمِيعَادَ ﴿١٩٤﴾

(187) Kuma ka tuna lokacin da Allah Ya ɗauki alkawari daga waɗanda aka bai wa Littafi cewa: “Lalle ku bayyana shi ga mutane, kuma kada ku ɓoye shi.” Sai suka jefar da shi can bayansu, kuma suka musanya shi da wani ɗan farashi kaɗan. To tir da abin da suke yin musanye da shi

(188) Kada ka yi tsammanin waɗanda suke yin farin ciki da irin abin da suka aikata, kuma suna son a riƙa yabon su da abin da ba su aikata ba, to kada ka yi tsammanin za su tsira daga azaba, kuma suna da azaba mai raɗaɗi

(189) Kuma ga Allah ne mulkin sammai da ƙasa yake. Kuma Allah Mai iko ne a kan komai

(190) Lalle a cikin halittar sammai da ƙasa da sassaɓawar dare da rana, tabbas akwai ayoyi ga ma’abota hankula

(191) Waɗanda suke ambaton Allah a tsaye da kuma zaune da kuma kishingiɗe, suna kuma tunani a kan halittar sammai da ƙasa, (suna cewa): “Ya Ubangijinmu, ba Ka halicci wannan a banza ba, tsarki ya tabbata gare Ka, Ka tserar da mu daga azabar wuta

(192) “Ya Ubangijinmu, lalle duk wanda Ka shigar da shi wuta, to haƙiƙa Ka kunyata shi; kuma azzalumai ba su da mai taimakon su

(193) “Ya Ubangijinmu, lalle mu mun ji wani mai kira yana yin kira zuwa imani cewa: “Ku yi imani da Ubangijinku;” sai muka yi imani. Ya Ubangijinmu, Ka gafarta mana zunubanmu, kuma Ka kankare mana kurakuranmu, kuma Ka karɓi rayukanmu tare da mutane masu ɗa’a

(194) “Ya Ubangijinmu, kuma Ka ba mu abin da Ka yi mana alƙawari da shi ta harshen manzanninka, kuma kada Ka kunyatar da mu ranar alƙiyama. Lalle Kai ba Ka saɓa alƙawari.”

فَٱسۡتَجَابَ لَهُمۡ رَبُّهُمۡ أَنِّي لَآ أُضِيعُ عَمَلَ عَٰمِلٖ مِّنكُم مِّن
ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ بَعۡضُكُم مِّنۢ بَعۡضٖۖ فَٱلَّذِينَ هَاجَرُواْ وَأُخۡرِجُواْ
مِن دِيَٰرِهِمۡ وَأُوذُواْ فِي سَبِيلِي وَقَٰتَلُواْ وَقُتِلُواْ لَأُكَفِّرَنَّ
عَنۡهُمۡ سَيِّـَٔاتِهِمۡ وَلَأُدۡخِلَنَّهُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا
ٱلۡأَنۡهَٰرُ ثَوَابٗا مِّنۡ عِندِ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ عِندَهُۥ حُسۡنُ ٱلثَّوَابِ ١٩٥
لَا يَغُرَّنَّكَ تَقَلُّبُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فِي ٱلۡبِلَٰدِ ١٩٦ مَتَٰعٞ قَلِيلٞ
ثُمَّ مَأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُۚ وَبِئۡسَ ٱلۡمِهَادُ ١٩٧ لَٰكِنِ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ
رَبَّهُمۡ لَهُمۡ جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا
نُزُلٗا مِّنۡ عِندِ ٱللَّهِۗ وَمَا عِندَ ٱللَّهِ خَيۡرٞ لِّلۡأَبۡرَارِ ١٩٨ وَإِنَّ مِنۡ
أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ لَمَن يُؤۡمِنُ بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيۡكُمۡ
وَمَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِمۡ خَٰشِعِينَ لِلَّهِ لَا يَشۡتَرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ
ثَمَنٗا قَلِيلًاۚ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ أَجۡرُهُمۡ عِندَ رَبِّهِمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ
سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ١٩٩ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱصۡبِرُواْ
وَصَابِرُواْ وَرَابِطُواْ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٢٠٠

سُورَةُ النِّسَاءِ

(195) Sai Ubangijinsu Ya amsa musu (cewa): “Lalle Ni ba zan tozarta aikin wani mai aiki daga cikinku ba, namiji ne ko mace; sashinku yana tare da sashe. To waɗanda suka yi hijira kuma aka fitar da su daga gidajensu kuma aka cutar da su wajen bin tafarkina kuma suka yi yaƙi kuma aka kashe su, lalle zan kankare musu kurakuransu, kuma lalle zan shigar da su gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. (Wannan) lada ne daga wajen Allah, kuma a wurin Allah ne mafi kyawun lada yake.”

(196) Kada zirga-zirgar kafirai a cikin garuruwa ta ruɗe ka

(197) Wani ɗan jin daɗi ne ƙanƙani, sannan makomarsu Jahannama. Kuma tir da wannan shimfiɗar

(198) Amma waɗanda suka bi dokokin Ubangijinsu suna da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za su dawwama a cikinsu, wannan liyafa ce ta musamman daga wajen Allah. Kuma abin da yake wajen Allah shi ne mafi alheri ga masu biyayya

(199) Kuma lalle a cikin Ma’abota Littafi, tabbas akwai waɗanda suke yin imani da Allah da kuma abin da aka saukar muku da kuma abin da aka saukar musu, suna masu ƙaskantar da kai ga Allah, ba sa musanya ayoyin Allah da wani ɗan farashi ƙanƙani. Waɗannan suna da lada a wajen Ubangijinsu. Lalle Allah Mai gaggawar hisabi ne

(200) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi haƙuri, kuma ku jure matuƙa ga yin haƙuri, kuma ku tsare iyakokin ƙasa, kuma ku kiyaye dokokin Allah don ku sami rabauta

Sura Nisa'i

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱتَّقُوا۟ رَبَّكُمُ ٱلَّذِى خَلَقَكُم مِّن نَّفْسٍ وَٰحِدَةٍ وَخَلَقَ مِنْهَا
زَوْجَهَا وَبَثَّ مِنْهُمَا رِجَالًا كَثِيرًا وَنِسَآءً ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ٱلَّذِى تَسَآءَلُونَ
بِهِۦ وَٱلْأَرْحَامَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلَيْكُمْ رَقِيبًا ﴿١﴾ وَءَاتُوا۟ ٱلْيَتَٰمَىٰٓ أَمْوَٰلَهُمْ ۖ
وَلَا تَتَبَدَّلُوا۟ ٱلْخَبِيثَ بِٱلطَّيِّبِ ۖ وَلَا تَأْكُلُوٓا۟ أَمْوَٰلَهُمْ إِلَىٰٓ أَمْوَٰلِكُمْ ۚ إِنَّهُۥ
كَانَ حُوبًا كَبِيرًا ﴿٢﴾ وَإِنْ خِفْتُمْ أَلَّا تُقْسِطُوا۟ فِى ٱلْيَتَٰمَىٰ فَٱنكِحُوا۟
مَا طَابَ لَكُم مِّنَ ٱلنِّسَآءِ مَثْنَىٰ وَثُلَٰثَ وَرُبَٰعَ ۖ فَإِنْ خِفْتُمْ أَلَّا تَعْدِلُوا۟
فَوَٰحِدَةً أَوْ مَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُمْ ۚ ذَٰلِكَ أَدْنَىٰٓ أَلَّا تَعُولُوا۟ ﴿٣﴾ وَءَاتُوا۟
ٱلنِّسَآءَ صَدُقَٰتِهِنَّ نِحْلَةً ۚ فَإِن طِبْنَ لَكُمْ عَن شَىْءٍ مِّنْهُ نَفْسًا فَكُلُوهُ
هَنِيٓـًٔا مَّرِيٓـًٔا ﴿٤﴾ وَلَا تُؤْتُوا۟ ٱلسُّفَهَآءَ أَمْوَٰلَكُمُ ٱلَّتِى جَعَلَ ٱللَّهُ لَكُمْ
قِيَٰمًا وَٱرْزُقُوهُمْ فِيهَا وَٱكْسُوهُمْ وَقُولُوا۟ لَهُمْ قَوْلًا مَّعْرُوفًا ﴿٥﴾ وَٱبْتَلُوا۟
ٱلْيَتَٰمَىٰ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغُوا۟ ٱلنِّكَاحَ فَإِنْ ءَانَسْتُم مِّنْهُمْ رُشْدًا فَٱدْفَعُوٓا۟
إِلَيْهِمْ أَمْوَٰلَهُمْ ۖ وَلَا تَأْكُلُوهَآ إِسْرَافًا وَبِدَارًا أَن يَكْبَرُوا۟ ۚ وَمَن كَانَ
غَنِيًّا فَلْيَسْتَعْفِفْ ۖ وَمَن كَانَ فَقِيرًا فَلْيَأْكُلْ بِٱلْمَعْرُوفِ ۚ فَإِذَا
دَفَعْتُمْ إِلَيْهِمْ أَمْوَٰلَهُمْ فَأَشْهِدُوا۟ عَلَيْهِمْ ۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ حَسِيبًا ﴿٦﴾

(1) Ya ku mutane, ku kiyaye dokokin Ubangijinku Wanda Ya halicce ku daga rai guda ɗaya, kuma Ya halicci matarsa daga shi, kuma Ya yaɗa maza da mata masu yawa daga gare su. Kuma ku kiyaye dokokin Allah Wanda kuke yi wa juna magiya da Shi, kuma ku kiyaye (yanke) zumunci. Lalle Allah Mai kula da ku ne

(2) Kuma ku bai wa marayu dukiyoyinsu; kuma kada ku musanya kyakkyawa da mummuna; kuma kada ku ci dukiyoyinsu haɗe da dukiyoyinku. Lalle yin hakan ya tabbata zunubi ne mai girma

(3) Kuma idan kun ji tsoron cewa ba za ku iya yin adalci ba dangane da marayu, to ku auri matan da kuke so, ko dai bibbiyu ko uku-uku ko kuma hurhuɗu. To idan kun ji tsoron ba za ku iya yin adalci ba, to sai ku taƙaita a kan ɗaya ko kuma abin da kuka mallaka na ƙwarƙwarori. Hakan shi ya fi nisanta ku daga zalunci

(4) Kuma ku bai wa mata sadakinsu kyauta. Amma idan suka ba ku wani abu cikin dadin rai, to ku ci shi yana mai daɗi da saukin haɗiya

(5) Kuma kada ku bai wa (marayu) wawaye dukiyoyinku wadda Allah Ya sanya rayuwarku take tsaye a kai, kuma ku ciyar da su, kuma ku tufatar da su daga cikinta, kuma ku faɗa musu magana mai daɗi

(6) Kuma ku jarraba hankulan marayu, har lokacin da suka isa aure, to idan kun ga alamar hankali tare da su, sai ku ba su dukiyoyinsu; kuma kada ku ci dukiyarsu ta hanyar almubazzaranci da kuma gaggawa don gudun kada su girma. Duk kuma wanda ya kasance mawadaci ne, to ya kame kansa; wanda kuma ya kasance mabuƙaci ne, to ya ci ta hanyar da ta dace. To idan za ku miƙa musu dukiyoyinsu, sai ku kafa musu shaidu. Kuma Allah Ya isa Mai hisabi

لِّلرِّجَالِ نَصِيبٌ مِّمَّا تَرَكَ ٱلْوَٰلِدَانِ وَٱلْأَقْرَبُونَ وَلِلنِّسَآءِ نَصِيبٌ
مِّمَّا تَرَكَ ٱلْوَٰلِدَانِ وَٱلْأَقْرَبُونَ مِمَّا قَلَّ مِنْهُ أَوْ كَثُرَ ۚ نَصِيبًا
مَّفْرُوضًا ﴿٧﴾ وَإِذَا حَضَرَ ٱلْقِسْمَةَ أُو۟لُوا۟ ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ
وَٱلْمَسَٰكِينُ فَٱرْزُقُوهُم مِّنْهُ وَقُولُوا۟ لَهُمْ قَوْلًا مَّعْرُوفًا
﴿٨﴾ وَلْيَخْشَ ٱلَّذِينَ لَوْ تَرَكُوا۟ مِنْ خَلْفِهِمْ ذُرِّيَّةً ضِعَٰفًا
خَافُوا۟ عَلَيْهِمْ فَلْيَتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَلْيَقُولُوا۟ قَوْلًا سَدِيدًا ﴿٩﴾ إِنَّ
ٱلَّذِينَ يَأْكُلُونَ أَمْوَٰلَ ٱلْيَتَٰمَىٰ ظُلْمًا إِنَّمَا يَأْكُلُونَ فِى
بُطُونِهِمْ نَارًا ۖ وَسَيَصْلَوْنَ سَعِيرًا ﴿١٠﴾ يُوصِيكُمُ ٱللَّهُ فِىٓ
أَوْلَٰدِكُمْ ۖ لِلذَّكَرِ مِثْلُ حَظِّ ٱلْأُنثَيَيْنِ ۚ فَإِن كُنَّ نِسَآءً
فَوْقَ ٱثْنَتَيْنِ فَلَهُنَّ ثُلُثَا مَا تَرَكَ ۖ وَإِن كَانَتْ وَٰحِدَةً فَلَهَا
ٱلنِّصْفُ ۚ وَلِأَبَوَيْهِ لِكُلِّ وَٰحِدٍ مِّنْهُمَا ٱلسُّدُسُ مِمَّا تَرَكَ إِن
كَانَ لَهُۥ وَلَدٌ ۚ فَإِن لَّمْ يَكُن لَّهُۥ وَلَدٌ وَوَرِثَهُۥٓ أَبَوَاهُ فَلِأُمِّهِ ٱلثُّلُثُ ۚ فَإِن
كَانَ لَهُۥٓ إِخْوَةٌ فَلِأُمِّهِ ٱلسُّدُسُ ۚ مِنۢ بَعْدِ وَصِيَّةٍ يُوصِى بِهَآ
أَوْ دَيْنٍ ۗ ءَابَآؤُكُمْ وَأَبْنَآؤُكُمْ لَا تَدْرُونَ أَيُّهُمْ أَقْرَبُ لَكُمْ
نَفْعًا ۚ فَرِيضَةً مِّنَ ٱللَّهِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمًا ﴿١١﴾

(7) Mazaje suna da wani kaso daga abin da mahaifa da dangi mafiya kusanci suka bari, haka mata su ma suna da wani kaso cikin abin da mahaifa da dangi mafiya kusanci suka bari, daga abin da yake ɗan kaɗan ko mai yawa. Kaso ne wanda an riga an rarraba shi

(8) Kuma idan dangi makusanta da marayu da mabuƙata suka halarci rabon gado, to ku arzurta su daga cikin wannan dukiya, kuma ku faɗa musu magana mai daɗi

(9) Waɗanda suke jin tsoron za su mutu su bar 'ya'ya raunana a bayansu, suna kuma jin tsoron a zalunce su, to su kiyaye dokokin Allah, kuma su faɗi magana ta daidai


(10) Lalle waɗanda suke cin dukiyar marayu bisa zalunci, wuta ce kawai suke ci a cikkunansu; kuma da sannu za su shiga wuta mai tsananin ƙuna

(11) Allah Yana yi muku wasiyya game da 'ya'yanku; namiji ɗaya yana da rabon 'ya'ya mata biyu. Amma idan sun kasance mata ne biyu ko fiye da biyu, to suna da kaso biyu bisa uku na abin da ya bari; kuma idan ta kasance 'ya ce guda ɗaya to tana da rabi. Kuma kowane ɗaya daga cikin mahaifansa biyu yana da kaso ɗaya bisa shida daga cikin abin da ya bari in ya kasance yana da ɗa ko 'ya[1]. Idan kuma ya kasance ba shi da ɗa ko 'ya, kuma mahaifansa biyu ne za su ci gadonsa, to mahaifiyarsa tana da kaso ɗaya bisa uku. Amma idan yana da 'yan'uwa[2], to mahaifiyarsa tana da kaso ɗaya bisa shida; bayan an fitar da wasiyyar da aka yi ko kuma bashi[3]. Iyayenku da 'ya'yanku, ba ku san daga cikinsu wane ne zai fi yi muku amfani ba. Rabo ne daga Allah. Lalle Allah Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai cikakkiyar hikima

(1) Ko kuma jika na ɓangaren 'ya'ya maza.

(2) Watau Shaƙiƙai ko li'abbai ko li'ummai.

(3) Ana fara fitar da bashi, sannan wasiyya wadda ba za ta wuce ɗaya bisa uku na dukiyar mamaci ba. Kuma babu wasiyya ga wanda yake da gado.


* وَلَكُمْ نِصْفُ مَا تَرَكَ أَزْوَٰجُكُمْ إِن لَّمْ يَكُن
لَّهُنَّ وَلَدٌ ۚ فَإِن كَانَ لَهُنَّ وَلَدٌ فَلَكُمُ ٱلرُّبُعُ مِمَّا
تَرَكْنَ ۚ مِنۢ بَعْدِ وَصِيَّةٍ يُوصِينَ بِهَآ أَوْ دَيْنٍ ۚ
وَلَهُنَّ ٱلرُّبُعُ مِمَّا تَرَكْتُمْ إِن لَّمْ يَكُن لَّكُمْ وَلَدٌ ۚ
فَإِن كَانَ لَكُمْ وَلَدٌ فَلَهُنَّ ٱلثُّمُنُ مِمَّا تَرَكْتُم ۚ
مِّنۢ بَعْدِ وَصِيَّةٍ تُوصُونَ بِهَآ أَوْ دَيْنٍ ۗ وَإِن كَانَ
رَجُلٌ يُورَثُ كَلَٰلَةً أَوِ ٱمْرَأَةٌ وَلَهُۥ أَخٌ أَوْ أُخْتٌ فَلِكُلِّ
وَٰحِدٍ مِّنْهُمَا ٱلسُّدُسُ ۚ فَإِن كَانُوٓا۟ أَكْثَرَ مِن ذَٰلِكَ
فَهُمْ شُرَكَآءُ فِى ٱلثُّلُثِ ۚ مِنۢ بَعْدِ وَصِيَّةٍ يُوصَىٰ
بِهَآ أَوْ دَيْنٍ ۙ غَيْرَ مُضَآرٍّ ۚ وَصِيَّةً مِّنَ ٱللَّهِ ۗ وَٱللَّهُ
عَلِيمٌ حَلِيمٌ ﴿١٢﴾ تِلْكَ حُدُودُ ٱللَّهِ ۚ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ
وَرَسُولَهُۥ يُدْخِلْهُ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا
ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۚ وَذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ
﴿١٣﴾ وَمَن يَعْصِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَتَعَدَّ حُدُودَهُۥ
يُدْخِلْهُ نَارًا خَٰلِدًا فِيهَا وَلَهُۥ عَذَابٌ مُّهِينٌ ﴿١٤﴾

(12) Kuma kuna da rabin abin da matanku suka bari in ya kasance ba su da ɗa ko 'ya, amma idan sun kasance suna da ɗa ko 'ya, to kuna da kaso ɗaya bisa huɗu na abin da suka bari, bayan zartar da wasiyyar da suka yi ko kuma bashi. Kuma suna da kaso ɗaya bisa huɗu[1] na abin da kuka bari, in ya kasance ba ku da ɗa ko 'ya. Amma idan ya kasance kuna da ɗa ko 'ya to (matanku) suna da kaso ɗaya cikin takwas na abin da kuka bari, bayan zartar da wasiyyar da kuka yi ko kuma bashi. Amma idan namiji ne za a gaje shi a matsayin kalala[2] ko mace, kuma yana da ɗan'uwa guda ɗaya ko 'yar'uwa guda ɗaya, to kowanne ɗaya yana da kaso ɗaya bisa shida. Amma idan sun fi haka yawa, to za su yi tarayya cikin kaso ɗaya bisa uku, bayan zartar da wasiyyar da aka yi ko kuma bashi, ba wanda zai cutar da (magadansa) ba. Allah Yana yi muku wasiyya matuƙar wasiyya. Allah kuma Mai cikakken sani ne, Mai haƙuri

(13) Waɗannan iyakoki ne na Allah. Wanda duk yake bin Allah da Manzonsa, to zai shigar da shi gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu. Kuma wannan shi ne rabo mai girma

(14) Wanda kuma yake saba wa Allah da Manzonsa, yake kuma ƙetare iyakokinsa, to zai shigar da shi wuta, yana mai dawwama a cikinta, kuma yana da wata azaba mai wulaƙantarwa

(1) Idan sama da mace ɗaya ce, to za su yi tarayya ne a cikin wannan kason.

(2) Kalala shi ne mamaci; namiji ko mace da bai bar 'ya'ya ko iyaye ba, sai 'yan'uwa.

وَٱلَّٰتِي يَأۡتِينَ ٱلۡفَٰحِشَةَ مِن نِّسَآئِكُمۡ فَٱسۡتَشۡهِدُواْ عَلَيۡهِنَّ
أَرۡبَعَةٗ مِّنكُمۡۖ فَإِن شَهِدُواْ فَأَمۡسِكُوهُنَّ فِي ٱلۡبُيُوتِ
حَتَّىٰ يَتَوَفَّىٰهُنَّ ٱلۡمَوۡتُ أَوۡ يَجۡعَلَ ٱللَّهُ لَهُنَّ سَبِيلٗا ١٥
وَٱلَّذَانِ يَأۡتِيَٰنِهَا مِنكُمۡ فَـَٔاذُوهُمَاۖ فَإِن تَابَا وَأَصۡلَحَا
فَأَعۡرِضُواْ عَنۡهُمَآۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ تَوَّابٗا رَّحِيمًا ١٦
إِنَّمَا ٱلتَّوۡبَةُ عَلَى ٱللَّهِ لِلَّذِينَ يَعۡمَلُونَ ٱلسُّوٓءَ بِجَهَٰلَةٖ
ثُمَّ يَتُوبُونَ مِن قَرِيبٖ فَأُوْلَٰٓئِكَ يَتُوبُ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡۗ
وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمٗا ١٧ وَلَيۡسَتِ ٱلتَّوۡبَةُ لِلَّذِينَ
يَعۡمَلُونَ ٱلسَّيِّـَٔاتِ حَتَّىٰٓ إِذَا حَضَرَ أَحَدَهُمُ ٱلۡمَوۡتُ
قَالَ إِنِّي تُبۡتُ ٱلۡـَٰٔنَ وَلَا ٱلَّذِينَ يَمُوتُونَ وَهُمۡ كُفَّارٌۚ
أُوْلَٰٓئِكَ أَعۡتَدۡنَا لَهُمۡ عَذَابًا أَلِيمٗا ١٨ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ لَا يَحِلُّ لَكُمۡ أَن تَرِثُواْ ٱلنِّسَآءَ كَرۡهٗاۖ وَلَا تَعۡضُلُوهُنَّ
لِتَذۡهَبُواْ بِبَعۡضِ مَآ ءَاتَيۡتُمُوهُنَّ إِلَّآ أَن يَأۡتِينَ بِفَٰحِشَةٖ
مُّبَيِّنَةٖۚ وَعَاشِرُوهُنَّ بِٱلۡمَعۡرُوفِۚ فَإِن كَرِهۡتُمُوهُنَّ فَعَسَىٰٓ
أَن تَكۡرَهُواْ شَيۡـٔٗا وَيَجۡعَلَ ٱللَّهُ فِيهِ خَيۡرٗا كَثِيرٗا ١٩

(15) Kuma waɗannan da suke aikata zina daga cikin matanku, to ku kafa musu shaidu guda huɗu daga cikinku, sannan idan sun bayar da shaida, to sai ku tsare su a cikin gidaje har sai mutuwa ta ɗauke su ko kuma Allah Ya sanya musu wata mafita[1]

(16) Kuma maza biyu daga cikinku da za su yi zina, to ku muzguna musu; amma idan sun tuba kuma suka gyara ayyukansu, to ku kawar da kai daga gare su. Lalle Allah Ya kasance Mai yawan karɓar tuba ne, Mai jin ƙai

(17) Tuban da Allah Yake karɓa kawai (ita ce) na waɗanda suke aikata mummunan aiki da jahilci, sannan su gaggauta tuba, to waɗannan Allah zai karɓi tubansu. Allah kuma Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai hikima

(18) Kuma ba a karɓar tuba daga waɗanda suke aikata munanan ayyuka har sai lokacin da mutuwa ta zo wa ɗayansu, sai ya ce: "Ni kam na tuba yanzu;" kuma ba a karɓar tuban waɗanda suke mutuwa alhalin suna kafirai. Waɗannan Mun yi musu tanadin azaba mai raɗaɗi

(19) Ya ku waɗanda suka yi imani, bai halatta gare ku ku gaji mata a bisa ga tilas ba; kuma kada ku hana su aure don ku ƙwace wani sashi na abin da kuka ba su, sai fa in sun zo da wata alfasha ta sarari. Kuma ku yi musu kyakkyawar mu'amala. Amma idan har kun ƙi su, to mai yiwuwa ne ku ƙi wani abu, Allah kuma Ya sanya alheri mai yawa a cikinsa

(1) Wannan hukuncin ya kasance ne gabanin a saukar da hukuncin bulala ɗari ga mazinatan da ba su taɓa yin aure ba ko jefewa ga waɗanda suka taɓa yin aure.

وَإِنْ أَرَدتُّمُ ٱسْتِبْدَالَ زَوْجٍ مَّكَانَ زَوْجٍ وَءَاتَيْتُمْ
إِحْدَىٰهُنَّ قِنطَارًا فَلَا تَأْخُذُوا۟ مِنْهُ شَيْـًٔا ۚ أَتَأْخُذُونَهُۥ
بُهْتَٰنًا وَإِثْمًا مُّبِينًا ﴿٢٠﴾ وَكَيْفَ تَأْخُذُونَهُۥ وَقَدْ أَفْضَىٰ
بَعْضُكُمْ إِلَىٰ بَعْضٍ وَأَخَذْنَ مِنكُم مِّيثَٰقًا غَلِيظًا
﴿٢١﴾ وَلَا تَنكِحُوا۟ مَا نَكَحَ ءَابَآؤُكُم مِّنَ ٱلنِّسَآءِ
إِلَّا مَا قَدْ سَلَفَ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ فَٰحِشَةً وَمَقْتًا وَسَآءَ
سَبِيلًا ﴿٢٢﴾ حُرِّمَتْ عَلَيْكُمْ أُمَّهَٰتُكُمْ وَبَنَاتُكُمْ
وَأَخَوَٰتُكُمْ وَعَمَّٰتُكُمْ وَخَٰلَٰتُكُمْ وَبَنَاتُ
ٱلْأَخِ وَبَنَاتُ ٱلْأُخْتِ وَأُمَّهَٰتُكُمُ ٱلَّٰتِىٓ أَرْضَعْنَكُمْ
وَأَخَوَٰتُكُم مِّنَ ٱلرَّضَٰعَةِ وَأُمَّهَٰتُ نِسَآئِكُمْ
وَرَبَٰٓئِبُكُمُ ٱلَّٰتِى فِى حُجُورِكُم مِّن نِّسَآئِكُمُ
ٱلَّٰتِى دَخَلْتُم بِهِنَّ فَإِن لَّمْ تَكُونُوا۟ دَخَلْتُم بِهِنَّ فَلَا
جُنَاحَ عَلَيْكُمْ وَحَلَٰٓئِلُ أَبْنَآئِكُمُ ٱلَّذِينَ مِنْ
أَصْلَٰبِكُمْ وَأَن تَجْمَعُوا۟ بَيْنَ ٱلْأُخْتَيْنِ إِلَّا
مَا قَدْ سَلَفَ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٢٣﴾

(20) Kuma idan kun yi nufin musanya wata mace a gurbin wata macen, kuma kun riga kun ba wa ɗayarsu dukiya mai yawa (ta sadaki), to kar ku karɓi komai daga cikinsa. Shin za ku karɓe shi ne a kan zalunci da laifi ƙarara?


(21) Kuma ta yaya za ku karɓe shi alhali kuma kun riga kun sadu da juna, kuma sun riƙi wani alƙawari mai ƙarfi daga wajenku?

(22) Kuma kada ku auri wadda iyayenku maza suka aure ta cikin mata, sai fa abin da ya riga ya shuɗe. Lalle yin hakan ya kasance alfasha ce kuma abu ne da zai jawo fushin Allah, kuma tafarki ne wanda ya yi muni

(23) An haramta muku auren iyayenku mata da 'ya'yanku mata da 'yan'uwanku mata da gwaggonninku da yagwalgwalanku da 'ya'yan ɗan'uwa da 'ya'yan 'yar'uwa da iyayenku waɗanda suka shayar da ku da 'yan'uwanku mata ta wajen shayarwa, da iyayen matanku(1) da agololinku waɗanda suke cikin gidajenku, waɗanda matan da kuka taɓa saduwa da su suka haife su, in kuwa ba ku taɓa saduwa da su ba, to babu laifi a kanku, da matan 'ya'yanku maza waɗanda suke na tsatsonku; haramun ne kuma ku haɗa 'yan'uwa mata biyu, sai dai abin da ya wuce a baya(2). Lalle Allah Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai jin ƙai

(1) Daga zarar an ɗaura auren mutum da mace, to uwarta ta haramta gare shi, ko ba su tare ba.

(2) Haramun ne mutum ya auri ya da ƙanwa lokaci ɗaya. Hakanan haramun ne ya haɗa mace da gwaggonta koinnarta lokaci ɗaya.



* وَٱلْمُحْصَنَٰتُ مِنَ ٱلنِّسَآءِ إِلَّا مَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُمْ ۖ
كِتَٰبَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ ۚ وَأُحِلَّ لَكُم مَّا وَرَآءَ ذَٰلِكُمْ أَن تَبْتَغُوا۟
بِأَمْوَٰلِكُم مُّحْصِنِينَ غَيْرَ مُسَٰفِحِينَ ۚ فَمَا ٱسْتَمْتَعْتُم بِهِۦ
مِنْهُنَّ فَـَٔاتُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ فَرِيضَةً ۚ وَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ فِيمَا
تَرَٰضَيْتُم بِهِۦ مِنۢ بَعْدِ ٱلْفَرِيضَةِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا
حَكِيمًا ﴿٢٤﴾ وَمَن لَّمْ يَسْتَطِعْ مِنكُمْ طَوْلًا أَن يَنكِحَ
ٱلْمُحْصَنَٰتِ ٱلْمُؤْمِنَٰتِ فَمِن مَّا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُم مِّن
فَتَيَٰتِكُمُ ٱلْمُؤْمِنَٰتِ ۚ وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِإِيمَٰنِكُمْ ۚ بَعْضُكُم
مِّنۢ بَعْضٍ ۚ فَٱنكِحُوهُنَّ بِإِذْنِ أَهْلِهِنَّ وَءَاتُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ
بِٱلْمَعْرُوفِ مُحْصَنَٰتٍ غَيْرَ مُسَٰفِحَٰتٍ وَلَا مُتَّخِذَٰتِ
أَخْدَانٍ ۚ فَإِذَآ أُحْصِنَّ فَإِنْ أَتَيْنَ بِفَٰحِشَةٍ فَعَلَيْهِنَّ نِصْفُ
مَا عَلَى ٱلْمُحْصَنَٰتِ مِنَ ٱلْعَذَابِ ۚ ذَٰلِكَ لِمَنْ خَشِىَ ٱلْعَنَتَ
مِنكُمْ ۚ وَأَن تَصْبِرُوا۟ خَيْرٌ لَّكُمْ ۗ وَٱللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ
﴿٢٥﴾ يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيُبَيِّنَ لَكُمْ وَيَهْدِيَكُمْ سُنَنَ ٱلَّذِينَ
مِن قَبْلِكُمْ وَيَتُوبَ عَلَيْكُمْ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿٢٦﴾

(24) Haka ma da matan aure, sai dai ƙwarafkwaranku; wannan hukuncin Allah ke nan a kanku. Kuma an halatta muku (sauran) matan da ba waɗannan ba, ku neme su da kuɗinku, kuna masu kame kanku, ba ma su zina ba. To waɗanda kuka sadu da su daga cikinsu ku ba su sadakinsu wanda kuka yanka musu. Kuma babu laifi a kanku game da abin da kuka yi yarjejeniya da shi bayan sadakin da kuka yanka. Lalle Allah Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai hikima

(25) Kuma daga cikinku wanda ba shi da yalwar dukiya da zai iya auren 'ya'ya muminai, to ya aura daga cikin abin da kuka mallaka na kuyanginku muminai. Kuma Allah Shi ne Mafi sanin imaninku. Sashinku 'yan'uwan sashi ne. To ku aure su da izinin iyayen gidansu. Sai ku ba su sadakinsu ta hanyar da ta dace, suna masu kame kawunansu ba mazinata ba, sannan ba waɗanda suke rifar farka a ɓoye ba. To idan sun yi aure, sannan suka yi zina, to abin da za a yi musu na azaba, shi ne rabin abin da ake yi wa 'ya'ya. Wannan ya shafi wanda ya ji tsoron matsatsi a cikinku. Amma ku yi haƙuri shi ya fi muku alheri. Allah kuma Mai yawan gafara ne, Mai jin ƙai

(26) Allah Yana nufin yi muku bayani ne, kuma Ya shiryar da ku hanyoyin waɗanda suka gabace ku, kuma Ya karɓi tubanku. Kuma Allah Mai yawan sani ne, Mai hikima

وَٱللَّهُ يُرِيدُ أَن يَتُوبَ عَلَيْكُمْ وَيُرِيدُ ٱلَّذِينَ يَتَّبِعُونَ
ٱلشَّهَوَٰتِ أَن تَمِيلُوا۟ مَيْلًا عَظِيمًا ﴿٢٧﴾ يُرِيدُ ٱللَّهُ أَن يُخَفِّفَ
عَنكُمْ ۚ وَخُلِقَ ٱلْإِنسَٰنُ ضَعِيفًا ﴿٢٨﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟
لَا تَأْكُلُوٓا۟ أَمْوَٰلَكُم بَيْنَكُم بِٱلْبَٰطِلِ إِلَّآ أَن تَكُونَ
تِجَٰرَةً عَن تَرَاضٍ مِّنكُمْ ۚ وَلَا تَقْتُلُوٓا۟ أَنفُسَكُمْ ۚ إِنَّ
ٱللَّهَ كَانَ بِكُمْ رَحِيمًا ﴿٢٩﴾ وَمَن يَفْعَلْ ذَٰلِكَ عُدْوَٰنًا
وَظُلْمًا فَسَوْفَ نُصْلِيهِ نَارًا ۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ
يَسِيرًا ﴿٣٠﴾ إِن تَجْتَنِبُوا۟ كَبَآئِرَ مَا تُنْهَوْنَ عَنْهُ نُكَفِّرْ
عَنكُمْ سَيِّـَٔاتِكُمْ وَنُدْخِلْكُم مُّدْخَلًا كَرِيمًا ﴿٣١﴾
وَلَا تَتَمَنَّوْا۟ مَا فَضَّلَ ٱللَّهُ بِهِۦ بَعْضَكُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ ۚ لِّلرِّجَالِ
نَصِيبٌ مِّمَّا ٱكْتَسَبُوا۟ ۖ وَلِلنِّسَآءِ نَصِيبٌ مِّمَّا ٱكْتَسَبْنَ ۚ
وَسْـَٔلُوا۟ ٱللَّهَ مِن فَضْلِهِۦٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِكُلِّ شَىْءٍ
عَلِيمًا ﴿٣٢﴾ وَلِكُلٍّ جَعَلْنَا مَوَٰلِىَ مِمَّا تَرَكَ ٱلْوَٰلِدَانِ
وَٱلْأَقْرَبُونَ ۚ وَٱلَّذِينَ عَقَدَتْ أَيْمَٰنُكُمْ فَـَٔاتُوهُمْ
نَصِيبَهُمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ شَهِيدًا ﴿٣٣﴾

(27) Kuma Allah Yana nufin Ya karɓi tubanku ne, amma waɗanda suke bin sha'awace-sha'awace, su kuma suna nufin ku karkace karkacewa mai girma

(28) Allah Yana nufin Ya sassauta muku. Kuma an halicci ɗan'adam mai rauni ne

(29) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ci dukiyoyinku a tsakaninku ta hanyar rashin gaskiya, sai dai in ya kasance kasuwanci ne bisa yarjejeniya a tsakaninku. Kuma kada ku kashe kawunanku. Lalle Allah Ya kasance Mai tausaya muku ne

(30) Kuma duk wanda ya aikata haka don ƙetare iyaka da zalunci, to za Mu shigar da shi cikin wata wuta; kuma yin haka ya kasance abu ne mai sauƙi a wurin Allah

(31) Idan har kun nisanci manya-manyan laifuffukan da aka hana ku, to za Mu kankare muku ƙananan kurakuranku, kuma za Mu shigar da ku wata mashiga ta karamci

(32) Kuma kada ku yi burin abin da Allah Ya fifita wasunku a kan wasu da shi, maza suna da kaso na abin da suka tsuwurwurta, haka mata ma suna da kaso na abin da suka tsuwurwurta. Kuma ku roƙi Allah daga falalarsa. Lalle Allah Ya kasance Masanin komai ne

(33) Kuma kowa Mun sanya masa magadansa daga abin da mahaifa suka bari ko dangi mafiya kusanci[1]. Su kuma waɗanda rantsuwar ƙulla (zumunci) ta haɗa tsakaninku, to ku ba su rabonsu[2]. Lalle Allah Ya kasance Mai tsinkaye ne a kan komai

(1) Ana nufin masu cin gado ta hanyar asibci.

(2) An shafe wannan hukuncin da aya ta 75 ta Suratul Anfal.

ٱلرِّجَالُ قَوَّٰمُونَ عَلَى ٱلنِّسَآءِ بِمَا فَضَّلَ ٱللَّهُ بَعْضَهُمْ عَلَىٰ
بَعْضٍ وَبِمَآ أَنفَقُوا۟ مِنْ أَمْوَٰلِهِمْ ۚ فَٱلصَّٰلِحَٰتُ قَٰنِتَٰتٌ
حَٰفِظَٰتٌ لِّلْغَيْبِ بِمَا حَفِظَ ٱللَّهُ ۚ وَٱلَّٰتِى تَخَافُونَ
نُشُوزَهُنَّ فَعِظُوهُنَّ وَٱهْجُرُوهُنَّ فِى ٱلْمَضَاجِعِ
وَٱضْرِبُوهُنَّ ۖ فَإِنْ أَطَعْنَكُمْ فَلَا تَبْغُوا۟ عَلَيْهِنَّ سَبِيلًا ۗ
إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيًّا كَبِيرًا ﴿٣٤﴾ وَإِنْ خِفْتُمْ شِقَاقَ بَيْنِهِمَا
فَٱبْعَثُوا۟ حَكَمًا مِّنْ أَهْلِهِۦ وَحَكَمًا مِّنْ أَهْلِهَآ إِن
يُرِيدَآ إِصْلَٰحًا يُوَفِّقِ ٱللَّهُ بَيْنَهُمَا ۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا
خَبِيرًا ﴿٣٥﴾ ۞ وَٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ وَلَا تُشْرِكُوا۟ بِهِۦ شَيْـًٔا ۖ
وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَٰنًا وَبِذِى ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينِ
وَٱلْجَارِ ذِى ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْجَارِ ٱلْجُنُبِ وَٱلصَّاحِبِ بِٱلْجَنۢبِ
وَٱبْنِ ٱلسَّبِيلِ وَمَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ
لَا يُحِبُّ مَن كَانَ مُخْتَالًا فَخُورًا ﴿٣٦﴾ ٱلَّذِينَ يَبْخَلُونَ
وَيَأْمُرُونَ ٱلنَّاسَ بِٱلْبُخْلِ وَيَكْتُمُونَ مَآ ءَاتَىٰهُمُ
ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ ۗ وَأَعْتَدْنَا لِلْكَٰفِرِينَ عَذَابًا مُّهِينًا ﴿٣٧﴾

(34) Maza su ne tsayayyu a kan mata saboda abin da Allah Ya fifita sashinsu da shi a kan sashi, kuma saboda abin da suka ciyar na dukiyarsu. To salihan mata masu ɗa'a ne, masu tsare (haƙƙokin mazajensu) ne a bayan idon mazajensu da tsarewar Allah. Waɗanda kuwa kuke jin tsoron kangarewarsu, to ku yi musu wa'azi, kuma ku ƙaurace musu a wuraren kwanciya, kuma ku doke su[1]; amma idan sun yi muku ɗa'a, to kada ku nemi wata hanyar cutar da su. Lalle Allah Ya kasance Maɗaukaki ne, Mai girma

(35) Kuma idan kun ji tsoron ci gaba da samun saɓani a tsakaninsu, to sai ku aika da wani mai hukunci daga danginsa (mijin), da wani mai hukunci daga danginta (matar), in (su mahukuntan) suna nufin samar da gyara, to Allah zai daidaita tsakaninsu (ma'auratan). Lalle Allah Ya kasance Mai yawan sani ne Masanin abin da yake ɓoye

(36) Kuma ku bauta wa Allah (Shi kaɗai), kada ku haɗa Shi da komai; kuma ku kyautata wa iyaye da dangi makusanta da marayu da talakawa da maƙwabci makusanci da maƙwabci na nesa, da abokin da ake tare[2] da kuma matafiyi da bayinku. Lalle Allah ba Ya son duk wanda ya kasance mai taƙama, mai yawan fariya

(37) Su ne waɗanda suke rowa kuma suke umartar mutane da rowa kuma suke ɓoye abin da Allah Ya ba su na falalarsa. Mun kuwa yi tanadin azaba mai wulaƙantarwa ga kafirai

(1) Watau duka wanda ba zai raunana jiki ba. Wannan mataki zai zo ne bayan duk wasu matakai na ladabtarwasun ci tura, sannan kuma ana da ƙwaƙƙwaran zaton cewa hakan zai wanzar da zaman lafiya tsakanin ma'aurata. Annabi ( ) bai taɓa dukan matarsa ko bawansa ba tunda yake.

(2) Watau wanda tafiya ta haɗa mutun da shi ko kuma matarsa.

وَٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمۡوَٰلَهُمۡ رِئَآءَ ٱلنَّاسِ وَلَا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ
وَلَا بِٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۗ وَمَن يَكُنِ ٱلشَّيۡطَٰنُ لَهُۥ قَرِينٗا فَسَآءَ
قَرِينٗا ٣٨ وَمَاذَا عَلَيۡهِمۡ لَوۡ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَأَنفَقُواْ
مِمَّا رَزَقَهُمُ ٱللَّهُۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِهِمۡ عَلِيمًا ٣٩ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَظۡلِمُ
مِثۡقَالَ ذَرَّةٖۖ وَإِن تَكُ حَسَنَةٗ يُضَٰعِفۡهَا وَيُؤۡتِ مِن لَّدُنۡهُ
أَجۡرًا عَظِيمٗا ٤٠ فَكَيۡفَ إِذَا جِئۡنَا مِن كُلِّ أُمَّةِۭ بِشَهِيدٖ
وَجِئۡنَا بِكَ عَلَىٰ هَٰٓؤُلَآءِ شَهِيدٗا ٤١ يَوۡمَئِذٖ يَوَدُّ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ وَعَصَوُاْ ٱلرَّسُولَ لَوۡ تُسَوَّىٰ بِهِمُ ٱلۡأَرۡضُ وَلَا يَكۡتُمُونَ
ٱللَّهَ حَدِيثٗا ٤٢ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقۡرَبُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَأَنتُمۡ
سُكَٰرَىٰ حَتَّىٰ تَعۡلَمُواْ مَا تَقُولُونَ وَلَا جُنُبًا إِلَّا عَابِرِي
سَبِيلٍ حَتَّىٰ تَغۡتَسِلُواْۚ وَإِن كُنتُم مَّرۡضَىٰٓ أَوۡ عَلَىٰ سَفَرٍ أَوۡ جَآءَ
أَحَدٞ مِّنكُم مِّنَ ٱلۡغَآئِطِ أَوۡ لَٰمَسۡتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَلَمۡ تَجِدُواْ مَآءٗ
فَتَيَمَّمُواْ صَعِيدٗا طَيِّبٗا فَٱمۡسَحُواْ بِوُجُوهِكُمۡ وَأَيۡدِيكُمۡۗ
إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَفُوًّا غَفُورًا ٤٣ أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ أُوتُواْ نَصِيبٗا مِّنَ
ٱلۡكِتَٰبِ يَشۡتَرُونَ ٱلضَّلَٰلَةَ وَيُرِيدُونَ أَن تَضِلُّواْ ٱلسَّبِيلَ ٤٤

(38) Waɗanda kuma suke ciyar da dukiyoyinsu don mutane su gani, kuma ba sa yin imani da Allah, ba sa kuma yin imani da ranar ƙarshe. Duk wanda Shaiɗan ya kasance shi ne abokinsa, to tir da aboki irin wannan

(39) Kuma me zai cutar da su da a ce sun yi imani da Allah da ranar ƙarshe, kuma suka ciyar daga abin da Allah Ya arzurta su da shi? Kuma Allah Ya kasance Mai yawan sani ne gare su

(40) Lalle Allah ba Ya zalunci ko da daidai da nauyin jaririyar tururuwa; kuma idan ya kasance aiki ne mai kyau to zai ninka shi, kuma Ya ba da lada mai girma daga wurinsa

(41) To yaya al'amarin zai kasance idan Muka zo da kowace al'umma tare da mai yi mata shaida, kai kuma Muka zo da kai a matsayin mai shaida kan waɗannan al'ummar?

(42) A wannan yini ne waɗanda suka kafirta kuma suka saɓa wa Manzo, za su yi burin ina ma a mayar da su ƙasa, kuma ba za su ɓoye wa Allah wani zance ba

(43) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku kusanci salla alhalin kuna cikin maye har sai kun san abin da kuke faɗa[1], haka mai janaba, sai dai in masu ƙetara hanya ne, har sai kun yi wanka. Idan kuma kun kasance marasa lafiya ko a halin tafiya, ko ɗaya daga cikinku ya dawo daga bahaya ko kuma kuka sadu da mata kuma ba ku sami ruwa ba, to sai ku nufi doron ƙasa mai tsarki ku yi taimama, sai ku shafi fuskokinku da hannayenku. Lalle Allah Ya kasance Mai afuwa ne, Mai gafara

(44) Shin ba ka ga waɗannan da aka ba su wani rabo na ilimin Littafi ba, suna sayen ɓata, kuma suna nufin su ga kun ɓace daga kan hanya?

(1) Wannan ayar an shafe ta da ayar haramta shan giya baki ɗaya da ke cikin Suratun Ma'idah, aya ta 90.


وَٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِأَعۡدَآئِكُمۡۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَلِيّٗا وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ نَصِيرٗا ٤٥
مِّنَ ٱلَّذِينَ هَادُواْ يُحَرِّفُونَ ٱلۡكَلِمَ عَن مَّوَاضِعِهِۦ وَيَقُولُونَ
سَمِعۡنَا وَعَصَيۡنَا وَٱسۡمَعۡ غَيۡرَ مُسۡمَعٖ وَرَٰعِنَا لَيَّۢا بِأَلۡسِنَتِهِمۡ
وَطَعۡنٗا فِي ٱلدِّينِۚ وَلَوۡ أَنَّهُمۡ قَالُواْ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَا وَٱسۡمَعۡ وَٱنظُرۡنَا
لَكَانَ خَيۡرٗا لَّهُمۡ وَأَقۡوَمَ وَلَٰكِن لَّعَنَهُمُ ٱللَّهُ بِكُفۡرِهِمۡ فَلَا يُؤۡمِنُونَ
إِلَّا قَلِيلٗا ٤٦ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ ءَامِنُواْ بِمَا نَزَّلۡنَا
مُصَدِّقٗا لِّمَا مَعَكُم مِّن قَبۡلِ أَن نَّطۡمِسَ وُجُوهٗا فَنَرُدَّهَا
عَلَىٰٓ أَدۡبَارِهَآ أَوۡ نَلۡعَنَهُمۡ كَمَا لَعَنَّآ أَصۡحَٰبَ ٱلسَّبۡتِۚ وَكَانَ أَمۡرُ
ٱللَّهِ مَفۡعُولًا ٤٧ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ
ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱفۡتَرَىٰٓ إِثۡمًا عَظِيمًا
٤٨ أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ يُزَكُّونَ أَنفُسَهُم بَلِ ٱللَّهُ يُزَكِّي مَن يَشَآءُ
وَلَا يُظۡلَمُونَ فَتِيلًا ٤٩ ٱنظُرۡ كَيۡفَ يَفۡتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَۖ
وَكَفَىٰ بِهِۦٓ إِثۡمٗا مُّبِينًا ٥٠ أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ أُوتُواْ نَصِيبٗا
مِّنَ ٱلۡكِتَٰبِ يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡجِبۡتِ وَٱلطَّٰغُوتِ وَيَقُولُونَ
لِلَّذِينَ كَفَرُواْ هَٰٓؤُلَآءِ أَهۡدَىٰ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ سَبِيلًا ٥١

(45) Allah kuma Shi ne mafi sanin maƙiyanku. Kuma Allah Ya isa Ya zama majiɓinci (gare ku), kuma Ya isa Ya zama Mai taimako (gare ku)

(46) Cikin waɗanda suka zama Yahudawa akwai waɗanda suke juyar da kalmomi daga bigirensu, kuma suna cewa: "Mun ji, kuma mun saba, kuma ka saurara, kai ba abin a saurare ka ba ne, kuma 'ra'ina'."[1] Suna masu karkatar da harashensu kuma don su soki addini. Da za su ce: "Mun ji, mun yi ɗa'a, kuma ka saurare mu, kuma ka jira mu." da ya kasance mafi alheri gare su, kuma ya fi zama miƙaƙƙiyar (hanya), sai dai Allah Ya riga Ya tsine musu saboda kafircinsu, ba za su yi imani ba sai kaɗan

(47) Ya ku waɗanda aka ba su littafi, ku yi imani da abin da Muka saukar mai gaskata abin da yake tare da ku, tun kafin Mu shafe wasu fuskoki, Mu mayar da su bayansu, ko kuma Mu la'ance su irin yadda Muka la'anci ma'abota ranar Asabar[2]. Kuma al'amarin Allah ya kasance abin zartarwa ne

(48) Lalle Allah ba Ya gafarta a yi shirka da Shi, amma Yana gafarta abin da bai kai shirka ba ga wanda Ya ga dama. Kuma duk wanda ya yi shirka da Allah, to haƙiƙa ya ƙirƙiri wani gagarumin laifi

(49) Shin ba ka ganin waɗannan da suke tsarkake kawunansu? Ba haka ba ne, Allah ne Yake tsarkake wanda Ya ga dama, kuma ba za a zalunce su ba ko da gwargwadon zaren ƙwallon dabino ne

(50) Duba ka ga yadda suke ƙirƙirar ƙarya su jingina wa Allah; kuma yin haka kaɗai ya isa zama wani zunubi mabayyani

(51) Shin ba ka ganin waɗanda aka ba su wani rabo na ilimin Littafi, suna yin imani da Jibtu da Dagutu, kuma suna faɗa wa waɗanda suka kafirta cewa: "Waɗannan su suka fi waɗanda suka yi imani shiriya."?

(1) Duba Suratul Baƙara, aya ta 104.

(2) Su ne Yahuduwa waɗanda Allah ya hana su kamun kifi duk ranar Assabar, amma sai suka riƙa yin dabara suna saɓawa umarninsa. Duba Suratul A'araf, aya ta 163-166.

أُولَٰئِكَ ٱلَّذِينَ لَعَنَهُمُ ٱللَّهُ ۖ وَمَن يَلْعَنِ ٱللَّهُ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ نَصِيرًا ﴿٥٢﴾
أَمْ لَهُمْ نَصِيبٌ مِّنَ ٱلْمُلْكِ فَإِذًا لَّا يُؤْتُونَ ٱلنَّاسَ نَقِيرًا ﴿٥٣﴾ أَمْ
يَحْسُدُونَ ٱلنَّاسَ عَلَىٰ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ ۖ فَقَدْ ءَاتَيْنَآ
ءَالَ إِبْرَٰهِيمَ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ وَءَاتَيْنَٰهُم مُّلْكًا عَظِيمًا ﴿٥٤﴾
فَمِنْهُم مَّنْ ءَامَنَ بِهِۦ وَمِنْهُم مَّن صَدَّ عَنْهُ ۚ وَكَفَىٰ بِجَهَنَّمَ سَعِيرًا ﴿٥٥﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا سَوْفَ نُصْلِيهِمْ نَارًا كُلَّمَا نَضِجَتْ
جُلُودُهُم بَدَّلْنَٰهُمْ جُلُودًا غَيْرَهَا لِيَذُوقُوا۟ ٱلْعَذَابَ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ
عَزِيزًا حَكِيمًا ﴿٥٦﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَنُدْخِلُهُمْ
جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۖ لَّهُمْ فِيهَآ
أَزْوَٰجٌ مُّطَهَّرَةٌ ۖ وَنُدْخِلُهُمْ ظِلًّا ظَلِيلًا ﴿٥٧﴾ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ يَأْمُرُكُمْ
أَن تُؤَدُّوا۟ ٱلْأَمَٰنَٰتِ إِلَىٰٓ أَهْلِهَا وَإِذَا حَكَمْتُم بَيْنَ ٱلنَّاسِ أَن
تَحْكُمُوا۟ بِٱلْعَدْلِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ نِعِمَّا يَعِظُكُم بِهِۦٓ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ سَمِيعًۢا
بَصِيرًا ﴿٥٨﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَطِيعُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُوا۟ ٱلرَّسُولَ وَأُو۟لِى
ٱلْأَمْرِ مِنكُمْ ۖ فَإِن تَنَٰزَعْتُمْ فِى شَىْءٍ فَرُدُّوهُ إِلَى ٱللَّهِ وَٱلرَّسُولِ إِن كُنتُمْ
تُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ ۚ ذَٰلِكَ خَيْرٌ وَأَحْسَنُ تَأْوِيلًا ﴿٥٩﴾

(52) Wadanda su ne wadanda Allah Ya la'ance su; duk kuwa wanda Allah Ya la'anta, to ba za ka taba sama masa wani mataimaki ba

(53) Shin suna da wani kaso ne na mulki? To da haka ne da kuwa ba za su ba wa mutane ko da gwargwadon digon bayan dabino ba

(54) Shin yanzu za su rika yi wa mutane hassada ne a kan abin da Allah Ya ba su na falalarsa? To hakika Mun bai wa zurriyar gidan Ibrahimu Littafi da kuma hikima, kuma Mun ba su wani mulki mai girma

(55) To daga cikinsu akwai wanda ya yi imani da shi, kuma daga cikinsu akwai wanda ya bijire masa. Jahannama kuwa ta isa wurin kuna (56) Lalle wadanda suka kafirce wa ayoyinmu, za Mu shigar da su wata wuta, duk lokacin da fatunsu suka kone, sai Mu musanya musu da wasu fatun daban, don su dandani azaba. Lalle Allah Ya kasance Mabuwayi ne, Mai hikima

(57) Wadanda suka yi imani kuwa, kuma suka yi aiki nagari, to za Mu shigar da su gidajen Aljanna wadanda koramu suke gudana ta karkashinsu, suna masu dawwama a cikinsu har abada; suna da mata tsarkaka a cikinsu; kuma za Mu shigar da su cikin wata inuwa, inuwa mayalwaciya marar gushewa

(58) Lalle Allah Yana umartar ku da ku mayar da amanoni ga masu su, kuma idan za ku yi hukunci a tsakanin mutane, to ku yi hukunci da adalci. Lalle kam madalla da abin da Allah Yake muku wa'azi da shi. Lalle Allah Ya kasance Mai ji ne, Mai gani

(59) Ya ku wadanda suka yi imani, ku yi da'a ga Allah, kuma ku yi da'a ga Manzo da kuma majibinta lamarinku. Idan kun yi jayayya a kan wani abu, to ku mayar da shi zuwa ga Allah da Manzonsa in kun kasance kun yi imani da Allah da ranar karshe. Wannan shi ne mafi alheri, kuma mafi kyan makoma

أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ يَزْعُمُونَ أَنَّهُمْ ءَامَنُوا۟ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيْكَ
وَمَآ أُنزِلَ مِن قَبْلِكَ يُرِيدُونَ أَن يَتَحَاكَمُوٓا۟ إِلَى ٱلطَّٰغُوتِ
وَقَدْ أُمِرُوٓا۟ أَن يَكْفُرُوا۟ بِهِۦ ۖ وَيُرِيدُ ٱلشَّيْطَٰنُ أَن يُضِلَّهُمْ
ضَلَٰلًۢا بَعِيدًا ﴿٦٠﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ تَعَالَوْا۟ إِلَىٰ مَآ أَنزَلَ
ٱللَّهُ وَإِلَى ٱلرَّسُولِ رَأَيْتَ ٱلْمُنَٰفِقِينَ يَصُدُّونَ عَنكَ
صُدُودًا ﴿٦١﴾ فَكَيْفَ إِذَآ أَصَٰبَتْهُم مُّصِيبَةٌۢ بِمَا
قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ ثُمَّ جَآءُوكَ يَحْلِفُونَ بِٱللَّهِ إِنْ أَرَدْنَآ إِلَّآ
إِحْسَٰنًا وَتَوْفِيقًا ﴿٦٢﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ يَعْلَمُ ٱللَّهُ مَا
فِى قُلُوبِهِمْ فَأَعْرِضْ عَنْهُمْ وَعِظْهُمْ وَقُل لَّهُمْ فِىٓ
أَنفُسِهِمْ قَوْلًۢا بَلِيغًا ﴿٦٣﴾ وَمَآ أَرْسَلْنَا مِن رَّسُولٍ إِلَّا
لِيُطَاعَ بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۚ وَلَوْ أَنَّهُمْ إِذ ظَّلَمُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ
جَآءُوكَ فَٱسْتَغْفَرُوا۟ ٱللَّهَ وَٱسْتَغْفَرَ لَهُمُ ٱلرَّسُولُ
لَوَجَدُوا۟ ٱللَّهَ تَوَّابًا رَّحِيمًا ﴿٦٤﴾ فَلَا وَرَبِّكَ لَا يُؤْمِنُونَ
حَتَّىٰ يُحَكِّمُوكَ فِيمَا شَجَرَ بَيْنَهُمْ ثُمَّ لَا يَجِدُوا۟ فِىٓ
أَنفُسِهِمْ حَرَجًا مِّمَّا قَضَيْتَ وَيُسَلِّمُوا۟ تَسْلِيمًا ﴿٦٥﴾

(60) Shin ba ka ganin waɗannan da suke riya cewa sun yi imani da abin da aka saukar maka, da abin da aka saukar gabaninka, suna nufin su kai hukunci gaban Dagutu[1] (wanin Allah), alhalin an umarce su da su kafirce masa, Shaiɗan kuma yana nufin ya ɓatar da su ɓata mai nisa?

(61) Kuma idan an ce da su: "Ku zo ga abin da Allah Ya saukar, kuma ku zo ga wannan Manzo," sai kawai ka ga munafuƙai suna bijire maka matuƙar bijirewa

(62) To yaya halinsu zai kasance idan wata musiba ta sauka a kansu saboda abin da hannayensu suka gabatar, sannan sai su zo maka suna rantsuwa da Allah, (suna cewa): "Ba ma nufin wani abu sai kyautatawa da kuma haɗin kai."?

(63) Waɗannan su ne waɗanda Allah Yake sane da abin da ke cikin zukatansu, don haka ka kawar da kai daga kansu kuma ka yi musu wa'azi kuma ka faɗa musu magana a karan-kawunansu magana mai shiga zukata

(64) Kuma ba Mu taɓa aiko wani manzo ba, face sai don a yi masa ɗa'a da izinin Allah. Kuma da a ce lokacin da suka zalunci kawunansu sun zo maka, sun nemi Allah Ya gafarta musu, sannan Manzo ya roƙa musu gafara, to tabbas da sun sami Allah Yana Mai yawan karɓar tuba, Mai jin ƙai

(65) To ina rantsuwa da Ubangijinka, ba za su yi imani ba har sai sun kai hukunci a gabanka game da duk abin da ya faru na saɓani a tsakaninsu, sannan ba su ji wani ƙunci a cikin zukatansu ba game da abin da ka zartar na hukunci, kuma su miƙa wuya miƙawa gaba ɗaya

(1) Ɗagutu, shi ne duk wani abu da bawa zai ƙetare iyakokin Allah a sanadiyyarsa; mutum ne ko gunki ko wata doka.

وَلَوْ أَنَّا كَتَبْنَا عَلَيْهِمْ أَنِ ٱقْتُلُوٓا۟ أَنفُسَكُمْ أَوِ ٱخْرُجُوا۟ مِن
دِيَٰرِكُم مَّا فَعَلُوهُ إِلَّا قَلِيلٌ مِّنْهُمْ ۖ وَلَوْ أَنَّهُمْ فَعَلُوا۟ مَا يُوعَظُونَ
بِهِۦ لَكَانَ خَيْرًا لَّهُمْ وَأَشَدَّ تَثْبِيتًا ﴿٦٦﴾ وَإِذًا لَّـَٔاتَيْنَٰهُم
مِّن لَّدُنَّآ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿٦٧﴾ وَلَهَدَيْنَٰهُمْ صِرَٰطًا مُّسْتَقِيمًا
﴿٦٨﴾ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ فَأُو۟لَٰٓئِكَ مَعَ ٱلَّذِينَ أَنْعَمَ ٱللَّهُ
عَلَيْهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلصِّدِّيقِينَ وَٱلشُّهَدَآءِ وَٱلصَّٰلِحِينَ ۚ
وَحَسُنَ أُو۟لَٰٓئِكَ رَفِيقًا ﴿٦٩﴾ ذَٰلِكَ ٱلْفَضْلُ مِنَ ٱللَّهِ ۚ وَكَفَىٰ
بِٱللَّهِ عَلِيمًا ﴿٧٠﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ خُذُوا۟ حِذْرَكُمْ
فَٱنفِرُوا۟ ثُبَاتٍ أَوِ ٱنفِرُوا۟ جَمِيعًا ﴿٧١﴾ وَإِنَّ مِنكُمْ لَمَن لَّيُبَطِّئَنَّ
فَإِنْ أَصَٰبَتْكُم مُّصِيبَةٌ قَالَ قَدْ أَنْعَمَ ٱللَّهُ عَلَىَّ إِذْ لَمْ أَكُن
مَّعَهُمْ شَهِيدًا ﴿٧٢﴾ وَلَئِنْ أَصَٰبَكُمْ فَضْلٌ مِّنَ ٱللَّهِ لَيَقُولَنَّ كَأَن
لَّمْ تَكُۢنۢ بَيْنَكُمْ وَبَيْنَهُۥ مَوَدَّةٌ يَٰلَيْتَنِى كُنتُ مَعَهُمْ
فَأَفُوزَ فَوْزًا عَظِيمًا ﴿٧٣﴾ ۞ فَلْيُقَٰتِلْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ٱلَّذِينَ
يَشْرُونَ ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا بِٱلْءَاخِرَةِ ۚ وَمَن يُقَٰتِلْ فِى سَبِيلِ
ٱللَّهِ فَيُقْتَلْ أَوْ يَغْلِبْ فَسَوْفَ نُؤْتِيهِ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿٧٤﴾

(66) Kuma in da a ce lalle Mun wajabta musu cewa: "Ku kashe kawunanku ko ku fita daga gidajenku," da 'yan kaɗan ne daga cikinsu za su aikata hakan. Da a ce sun aikata abin da ake musu wa'azi da shi, to da ya fi alheri, kuma da ya fi tsananin tabbatar da su (a kan hanya madaidaiciya)

(67) Da sun yi hakan kuwa tabbas da Mun ba su wani babban lada daga wajenmu

(68) Kuma tabbas da Mun shiryar da su tafarki madaidaici

(69) Kuma duk waɗanda suka yi wa Allah ɗa'a da wannan Manzon, to waɗannan suna tare da waɗanda Allah Ya yi musu ni'ima, su ne annabawa da siddiƙai da shahidai da salihan bayi. Kuma madalla da waɗannan abokai

(70) Wannan falala ce daga Allah. Kuma Allah Ya isa masanin (dukkan lamura)

(71) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi taka-tsantsan, kuma ku fita ƙungiya-ƙungiya, ko kuma ku fita gaba ɗaya

(72) Kuma lalle a cikinku akwai wanda yake daƙilewa, idan wata musiba ta same ku, sai ya ce: "Haƙiƙa Allah Ya yi mini ni'ima da ban halarci (yaƙin) tare da su ba."

(73) Amma idan wata falala ta same ku daga Allah, tabbas zai riƙa cewa, kamar daɗai ba wata soyayya tsakaninku da shi: "Ina ma na kasance tare da su, don ni ma in rabauta rabo mai girma?"(1)

(74) To waɗanda suke sayen rayuwar lahira da ta duniya, sai su yi yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah. Duk wanda yake yin yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah kuwa, sai aka kashe shi ko kuma ya yi galaba, to za Mu ba shi lada mai girma

(1) Watau a raba ganimar da aka samo tare da shi, shi ma ya more sosai.

وَمَا لَكُمْ لَا تُقَٰتِلُونَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلْمُسْتَضْعَفِينَ مِنَ ٱلرِّجَالِ
وَٱلنِّسَآءِ وَٱلْوِلْدَٰنِ ٱلَّذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَآ أَخْرِجْنَا مِنْ هَٰذِهِ ٱلْقَرْيَةِ
ٱلظَّالِمِ أَهْلُهَا وَٱجْعَل لَّنَا مِن لَّدُنكَ وَلِيًّا وَٱجْعَل لَّنَا مِن لَّدُنكَ نَصِيرًا
٧٥ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ يُقَٰتِلُونَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ يُقَٰتِلُونَ فِى
سَبِيلِ ٱلطَّٰغُوتِ فَقَٰتِلُوٓا۟ أَوْلِيَآءَ ٱلشَّيْطَٰنِ ۖ إِنَّ كَيْدَ ٱلشَّيْطَٰنِ
كَانَ ضَعِيفًا ٧٦ أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ قِيلَ لَهُمْ كُفُّوٓا۟ أَيْدِيَكُمْ وَأَقِيمُوا۟
ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ فَلَمَّا كُتِبَ عَلَيْهِمُ ٱلْقِتَالُ إِذَا فَرِيقٌ مِّنْهُمْ
يَخْشَوْنَ ٱلنَّاسَ كَخَشْيَةِ ٱللَّهِ أَوْ أَشَدَّ خَشْيَةً ۚ وَقَالُوا۟ رَبَّنَا لِمَ كَتَبْتَ
عَلَيْنَا ٱلْقِتَالَ لَوْلَآ أَخَّرْتَنَآ إِلَىٰٓ أَجَلٍ قَرِيبٍ ۗ قُلْ مَتَٰعُ ٱلدُّنْيَا قَلِيلٌ
وَٱلْءَاخِرَةُ خَيْرٌ لِّمَنِ ٱتَّقَىٰ وَلَا تُظْلَمُونَ فَتِيلًا ٧٧ أَيْنَمَا تَكُونُوا۟
يُدْرِككُّمُ ٱلْمَوْتُ وَلَوْ كُنتُمْ فِى بُرُوجٍ مُّشَيَّدَةٍ ۗ وَإِن تُصِبْهُمْ حَسَنَةٌ
يَقُولُوا۟ هَٰذِهِۦ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ ۖ وَإِن تُصِبْهُمْ سَيِّئَةٌ يَقُولُوا۟ هَٰذِهِۦ مِنْ
عِندِكَ ۚ قُلْ كُلٌّ مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ ۖ فَمَالِ هَٰٓؤُلَآءِ ٱلْقَوْمِ لَا يَكَادُونَ يَفْقَهُونَ
حَدِيثًا ٧٨ مَّآ أَصَابَكَ مِنْ حَسَنَةٍ فَمِنَ ٱللَّهِ ۖ وَمَآ أَصَابَكَ مِن سَيِّئَةٍ
فَمِن نَّفْسِكَ ۚ وَأَرْسَلْنَٰكَ لِلنَّاسِ رَسُولًا ۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدًا ٧٩

(75) Kuma me ya same ku ne, da ba za ku yi yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah ba, da kuma kuɓutar da raunana maza da mata da yara ƙanana, waɗanda suke cewa: "Ya Ubangijinmu, Ka fitar da mu daga wannan alƙaryar wadda mutanenta suke azzalumai, kuma Ka sanya mana wani majiɓincin lamari daga wurinka, kuma Ka sanya mana wani mai taimako daga wurinka?"
(76) Waɗanda suka yi imani suna yaƙi ne don ɗaukaka kalmar Allah; waɗanda kuma suka kafirce suna yin yaƙi ne don kare Ɗagutu; to ku yaƙi masoya Shaiɗan; lalle makircin Shaiɗan rarrauna ne
(77) Shin ba ka ganin waɗanda aka ce da su: "Ku kame hannayenku kuma ku tsayar da salla kuma ku bayar da zakka?"[1] To yayin da aka wajabta musu yaƙi, sai ga wani ɓangare daga cikinsu suna jin tsoron mutane kamar yadda suke jin tsoron Allah, ko ma fiye da hakan. Kuma sai suka ce: "Ya Ubangijinmu, don me Ka wajabta mana yin yaƙi, me ya hana Ka jinkirta mana zuwa wani lokaci makusanci?" Ka ce: "Jin daɗin duniya kaɗan ne, lahira kuwa ita ce mafi alheri ga wanda ya yi taƙawa, kuma ba za a zalunce ku ba, ko da gwargwadon zaren ƙwallon dabino ne."
(78) Duk inda kuka kasance mutuwa za ta riske ku, ko da kuna cikin waɗansu ganuwoyi masu tsawo. Kuma idan wani kyakkyawan abu ya same su, sai su ce: "Wannan ai daga Allah ne." Idan kuma wani mummunan abu ya same su, sai su ce: "Wannan daga wajenka ne."[2] Ka ce: "Dukkansu daga Allah ne." Shin me ya sami waɗannan mutane ne ba sa kusa ma da su fahimci zance?
(79) Duk wani kyakkyawan abu da ya same ka, to daga Allah ne; duk kuma wani mummunan abu da ya same ka, to daga wajen ka ne[3]. Kuma Mun aiko ka Manzo ga mutane. Kuma Allah Ya isa Mai shaida (a kan haka)

(1) Watau wasu daga cikin sahabbai waɗanda suke ta roƙon a farlanta musu jihadi, amma ana nuna musu su bar wannan maganar, su dai tsayar da salla su ba da zakka.

(2) Watau sai su camfa Manzon Allah ( ) su ce saboda shi ne wannan masifar ta same su.

(3) Watau saboda laifukansa ne da zunubansa.

مَّن يُطِعِ ٱلرَّسُولَ فَقَدۡ أَطَاعَ ٱللَّهَۖ وَمَن تَوَلَّىٰ فَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ
عَلَيۡهِمۡ حَفِيظٗا ٨٠ وَيَقُولُونَ طَاعَةٞۖ فَإِذَا بَرَزُواْ مِنۡ عِندِكَ
بَيَّتَ طَآئِفَةٞ مِّنۡهُمۡ غَيۡرَ ٱلَّذِي تَقُولُۖ وَٱللَّهُ يَكۡتُبُ مَا يُبَيِّتُونَۖ
فَأَعۡرِضۡ عَنۡهُمۡ وَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلًا
٨١ أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ ٱلۡقُرۡءَانَۚ وَلَوۡ كَانَ مِنۡ عِندِ غَيۡرِ ٱللَّهِ
لَوَجَدُواْ فِيهِ ٱخۡتِلَٰفٗا كَثِيرٗا ٨٢ وَإِذَا جَآءَهُمۡ أَمۡرٞ مِّنَ ٱلۡأَمۡنِ
أَوِ ٱلۡخَوۡفِ أَذَاعُواْ بِهِۦۖ وَلَوۡ رَدُّوهُ إِلَى ٱلرَّسُولِ وَإِلَىٰٓ أُوْلِي ٱلۡأَمۡرِ
مِنۡهُمۡ لَعَلِمَهُ ٱلَّذِينَ يَسۡتَنۢبِطُونَهُۥ مِنۡهُمۡۗ وَلَوۡلَا فَضۡلُ ٱللَّهِ
عَلَيۡكُمۡ وَرَحۡمَتُهُۥ لَٱتَّبَعۡتُمُ ٱلشَّيۡطَٰنَ إِلَّا قَلِيلٗا ٨٣
فَقَٰتِلۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۚ لَا تُكَلَّفُ إِلَّا نَفۡسَكَۚ وَحَرِّضِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۖ
عَسَى ٱللَّهُ أَن يَكُفَّ بَأۡسَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْۚ وَٱللَّهُ أَشَدُّ بَأۡسٗا
وَأَشَدُّ تَنكِيلٗا ٨٤ مَّن يَشۡفَعۡ شَفَٰعَةً حَسَنَةٗ يَكُن لَّهُۥ
نَصِيبٞ مِّنۡهَاۖ وَمَن يَشۡفَعۡ شَفَٰعَةً سَيِّئَةٗ يَكُن لَّهُۥ كِفۡلٞ مِّنۡهَاۗ
وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ مُّقِيتًا ٨٥ وَإِذَا حُيِّيتُم بِتَحِيَّةٖ فَحَيُّواْ
بِأَحۡسَنَ مِنۡهَآ أَوۡ رُدُّوهَآۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٍ حَسِيبًا ٨٦

(80) Duk wanda ya yi wa wannan Manzo ɗa'a, to haƙiƙa ya yi wa Allah ɗa'a ne; wanda kuwa ya bijire, to ba Mu aiko ka a matsayin mai tsaron su ba
(81) Kuma sukan ce: "Ai ba mu da wani abu sai biyayya." To idan suka fita daga wajenka, sai wata ƙungiya daga cikinsu, su riƙa ƙulla wani abu daban cikin dare, sabanin abin da suke faɗa; Allah kuwa Yana rubuta duk wani abu da suke ƙullawa da daddare; to ka kawar da kai daga kansu, kuma ka dogara ga Allah. Allah kuwa Ya isa abin dogaro
(82) Shin ba za su yi zuzzurfan tunani game da (ayoyin) Alƙur'ani ba ne? Kuma da a ce ya kasance daga wajen wani yake ba Allah ba, tabbas da sun sami saɓani mai yawa a cikinsa
(83) Kuma idan wani lamari ya zo musu wanda ya shafi zaman lafiya ko tsoro, sai su yaɗa shi. Da a ce sun mayar da shi zuwa ga wannan Manzo da shugabanni daga cikinsu, da lalle wanɗanda suke bin ƙwaƙƙwafin al'amarin sun san (dacewar a yaɗa shi ko a'a). Kuma ba don falalar Allah da rahamarsa a gare ku ba, tabbas da kun bi Shaiɗan, in ban da 'yan kaɗan (daga cikinku)
(84) To ka yi yaƙi domin ɗaukaka kalmar Allah, ba a ɗora maka nauyin tilasta kowa ba sai kanka. Kuma ka zaburar da muminai; Allah zai dankwafe ƙarfin waɗanda suka kafirta; kuma Allah Shi ne Mafi tsananin ƙarfi, kuma Mafi tsananin uƙuba
(85) Duk wanda ya yi (ma wani) kyakkyawar alfarma, zai samu rabonsa na lada daga gare ta; kuma duk wanda ya yi wa wani mummunar alfarma, zai samu rabonsa na zunubi daga gare ta. Kuma Allah Ya kasance Mai kiyaye komai ne(1)
(86) Kuma idan an gaishe ku da wata gaisuwa, to ku amsa da gaisuwar da ta fi wadda aka yi muku kyau, ko ku mayar da irinta. Lalle Allah Ya kasance Mai hisabi ne a kan kowane abu

(1) Watau zai yi wa kowa sakamako gwargwadon aikinsa mai kyau ko mummuna.

ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۚ لَيَجْمَعَنَّكُمْ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ لَا رَيْبَ فِيهِ ۗ
وَمَنْ أَصْدَقُ مِنَ ٱللَّهِ حَدِيثًا ﴿٨٧﴾ * فَمَا لَكُمْ فِى ٱلْمُنَٰفِقِينَ
فِئَتَيْنِ وَٱللَّهُ أَرْكَسَهُم بِمَا كَسَبُوٓا۟ ۚ أَتُرِيدُونَ أَن تَهْدُوا۟ مَنْ
أَضَلَّ ٱللَّهُ ۖ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ سَبِيلًا ﴿٨٨﴾ وَدُّوا۟ لَوْ تَكْفُرُونَ
كَمَا كَفَرُوا۟ فَتَكُونُونَ سَوَآءً ۖ فَلَا تَتَّخِذُوا۟ مِنْهُمْ أَوْلِيَآءَ حَتَّىٰ
يُهَاجِرُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۚ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَخُذُوهُمْ وَٱقْتُلُوهُمْ حَيْثُ
وَجَدتُّمُوهُمْ ۖ وَلَا تَتَّخِذُوا۟ مِنْهُمْ وَلِيًّا وَلَا نَصِيرًا ﴿٨٩﴾ إِلَّا ٱلَّذِينَ
يَصِلُونَ إِلَىٰ قَوْمٍۭ بَيْنَكُمْ وَبَيْنَهُم مِّيثَٰقٌ أَوْ جَآءُوكُمْ حَصِرَتْ
صُدُورُهُمْ أَن يُقَٰتِلُوكُمْ أَوْ يُقَٰتِلُوا۟ قَوْمَهُمْ ۚ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ
لَسَلَّطَهُمْ عَلَيْكُمْ فَلَقَٰتَلُوكُمْ ۚ فَإِنِ ٱعْتَزَلُوكُمْ فَلَمْ يُقَٰتِلُوكُمْ
وَأَلْقَوْا۟ إِلَيْكُمُ ٱلسَّلَمَ فَمَا جَعَلَ ٱللَّهُ لَكُمْ عَلَيْهِمْ سَبِيلًا ﴿٩٠﴾
سَتَجِدُونَ ءَاخَرِينَ يُرِيدُونَ أَن يَأْمَنُوكُمْ وَيَأْمَنُوا۟ قَوْمَهُمْ ۖ كُلَّ
مَا رُدُّوٓا۟ إِلَى ٱلْفِتْنَةِ أُرْكِسُوا۟ فِيهَا ۚ فَإِن لَّمْ يَعْتَزِلُوكُمْ وَيُلْقُوٓا۟
إِلَيْكُمُ ٱلسَّلَمَ وَيَكُفُّوٓا۟ أَيْدِيَهُمْ فَخُذُوهُمْ وَٱقْتُلُوهُمْ حَيْثُ
ثَقِفْتُمُوهُمْ ۚ وَأُو۟لَٰٓئِكُمْ جَعَلْنَا لَكُمْ عَلَيْهِمْ سُلْطَٰنًا مُّبِينًا ﴿٩١﴾

(87) Allah, babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. Lalle zai tattara ku a ranar alƙiyama, wadda babu kokwanto a cikinsa. Kuma wane ne ya fi Allah gaskiyar zance?

(88) Shin me ya sa kuka kasu gida biyu dangane da lamarin munafukai[1], alhali Allah ne Ya mayar da su baya saboda abin da suka aikata?[2] Shin kuna nufin ku shiryar da wanda Allah Ya riga Ya ɓatar da shi ne? Duk wanda Allah Ya ɓatar da shi kuwa, to ba za ka iya samar masa wata mafita ba

(89) Sun yi fatan ina ma za ku kafirta kamar yadda suka kafirta, sai ku zama ɗaya. Don haka kar ku riƙi masoya a cikinsu har sai sun yi hijira don Allah. Idan kuwa suka juya baya, to ku kama su, kuma ku kashe su a duk inda kuka same su; kuma kada ku riƙi wani masoyi ko mai taimako daga cikinsu

(90) Sai dai (ban da) waɗanda suke fakewa a wajen waɗansu mutane da kuke da yarjejeniya ta zaman lafiya a tsakaninku (da su), ko kuma waɗanda suka zo muku zukatansu sun ƙuntata game da yaƙar ku ko yaƙar mutanensu. Da kuwa Allah Ya ga dama da Ya ɗora su a kanku, kuma tabbas da sun yaƙe ku. Don haka idan suka bar ku ba su yaƙe ku ba, kuma suka miƙa muku saƙo na sulhu, to Allah bai ba ku wata dama ta ku yaƙe su ba

(91) Za ku sami wasu mutanen suna ƙoƙarin su sami amincewarku, kuma su sami amincewar mutanensu, amma duk sa'adda aka kira su zuwa kafirci sai su auka cikinsa. To idan ba su rabu da ku ba, kuma ba su neme ku da zaman lafiya ba, kuma ba su kame hannayensu ba, to ku kama su, kuma ku kashe su a duk inda kuka same su. Waɗannan kuwa Mun sanya muku bayyananniyar hujja a kansu

(1) Watau wasu daga cikin muminai suna kafirta su wasu kuma ba sa kafirta su.

(2) Watau na rashin biyayya da ɗa'a ga Allah da Manzonsa ( ).

وَمَا كَانَ لِمُؤْمِنٍ أَن يَقْتُلَ مُؤْمِنًا إِلَّا خَطَـًٔا ۚ وَمَن قَتَلَ
مُؤْمِنًا خَطَـًٔا فَتَحْرِيرُ رَقَبَةٍ مُّؤْمِنَةٍ وَدِيَةٌ مُّسَلَّمَةٌ
إِلَىٰٓ أَهْلِهِۦٓ إِلَّآ أَن يَصَّدَّقُوا۟ ۚ فَإِن كَانَ مِن قَوْمٍ عَدُوٍّ
لَّكُمْ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَتَحْرِيرُ رَقَبَةٍ مُّؤْمِنَةٍ ۖ وَإِن كَانَ
مِن قَوْمٍۭ بَيْنَكُمْ وَبَيْنَهُم مِّيثَٰقٌ فَدِيَةٌ مُّسَلَّمَةٌ إِلَىٰٓ
أَهْلِهِۦ وَتَحْرِيرُ رَقَبَةٍ مُّؤْمِنَةٍ ۖ فَمَن لَّمْ يَجِدْ فَصِيَامُ
شَهْرَيْنِ مُتَتَابِعَيْنِ تَوْبَةً مِّنَ ٱللَّهِ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ
عَلِيمًا حَكِيمًا ﴿٩٢﴾ وَمَن يَقْتُلْ مُؤْمِنًا مُّتَعَمِّدًا
فَجَزَآؤُهُۥ جَهَنَّمُ خَٰلِدًا فِيهَا وَغَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيْهِ
وَلَعَنَهُۥ وَأَعَدَّ لَهُۥ عَذَابًا عَظِيمًا ﴿٩٣﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوٓا۟ إِذَا ضَرَبْتُمْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ فَتَبَيَّنُوا۟ وَلَا تَقُولُوا۟
لِمَنْ أَلْقَىٰٓ إِلَيْكُمُ ٱلسَّلَٰمَ لَسْتَ مُؤْمِنًا تَبْتَغُونَ
عَرَضَ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا فَعِندَ ٱللَّهِ مَغَانِمُ كَثِيرَةٌ ۚ
كَذَٰلِكَ كُنتُم مِّن قَبْلُ فَمَنَّ ٱللَّهُ عَلَيْكُمْ
فَتَبَيَّنُوٓا۟ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرًا ﴿٩٤﴾

(92) Kuma bai dace ga mumini ya kashe wani mumini ba, sai bisa kuskure. Wanda ya kashe mumini bisa ga kuskure, to zai 'yanta bawa ko baiwa mumina da kuma diyya wadda za a mika wa iyalinsa, sai fa idan sun yafe. Amma idan wanda aka kashe yana cikin mutanen da suke makiyanku, alhalin kuma shi mumini ne, to za ku 'yanta bawa ko baiwa mumina; idan kuwa ya kasance yana cikin mutanen da kuke da yarjejeniyar zaman lafiya da su, to za a bayar da diyya wadda za a mika wa iyalinsa, sannan za ku 'yanta bawa ko baiwa mumina; wanda kuwa bai sami ikon haka ba, to sai ya yi azumin wata biyu a jere[1] don tuba zuwa ga Allah. Allah kuwa Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai hikima

(93) Duk kuwa wanda ya kashe mumini da gangan, to sakamakonsa wutar Jahannama ce, yana mai dawwama a cikinta, kuma Allah Ya yi fushi da shi, kuma Ya la'ance shi, kuma Ya yi masa tanadin azaba mai girma

(94) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka fita yaki don ɗaukaka kalmar Allah, to ku rika bincike, kuma kada ku ce ma wanda ya yi muku sallama: "Kai ba mumini ba ne,"[2] don kawai kuna neman wani jin dadi na rayuwar duniya, to a wurin Allah ne ganimomi masu yawa suke. Kamar haka ku ma a da kuka kasance[3], sai Allah Ya yi muku baiwa, don haka ku rika bincike. Lalle Allah Ya kasance Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne

(1) Watau sai dai idan akwai wani uzuri na rashin lafiya, ko na shari'a kamar shigowar Ramadana ko a ranar salla.

(2) Watau su ɗauke shi kawai a matsayin wanda yake ƙoƙarin kare kansa amma ba da gaske yake ba.

(3) Watau suna ɓoye imaninsu daga mutanensu mushirikai har Allah ya ba su ikon bayyana addininsu.

لَّا يَسْتَوِي ٱلْقَٰعِدُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ غَيْرُ أُو۟لِى ٱلضَّرَرِ وَٱلْمُجَٰهِدُونَ
فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ ۚ فَضَّلَ ٱللَّهُ ٱلْمُجَٰهِدِينَ بِأَمْوَٰلِهِمْ
وَأَنفُسِهِمْ عَلَى ٱلْقَٰعِدِينَ دَرَجَةً ۚ وَكُلًّا وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلْحُسْنَىٰ ۚ وَفَضَّلَ ٱللَّهُ
ٱلْمُجَٰهِدِينَ عَلَى ٱلْقَٰعِدِينَ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿٩٥﴾ دَرَجَٰتٍ مِّنْهُ وَمَغْفِرَةً
وَرَحْمَةً ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٩٦﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَوَفَّىٰهُمُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ
ظَالِمِىٓ أَنفُسِهِمْ قَالُوا۟ فِيمَ كُنتُمْ ۖ قَالُوا۟ كُنَّا مُسْتَضْعَفِينَ فِى ٱلْأَرْضِ ۚ
قَالُوٓا۟ أَلَمْ تَكُنْ أَرْضُ ٱللَّهِ وَٰسِعَةً فَتُهَاجِرُوا۟ فِيهَا ۚ فَأُو۟لَٰٓئِكَ مَأْوَىٰهُمْ
جَهَنَّمُ ۖ وَسَآءَتْ مَصِيرًا ﴿٩٧﴾ إِلَّا ٱلْمُسْتَضْعَفِينَ مِنَ ٱلرِّجَالِ
وَٱلنِّسَآءِ وَٱلْوِلْدَٰنِ لَا يَسْتَطِيعُونَ حِيلَةً وَلَا يَهْتَدُونَ سَبِيلًا ﴿٩٨﴾
فَأُو۟لَٰٓئِكَ عَسَى ٱللَّهُ أَن يَعْفُوَ عَنْهُمْ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَفُوًّا غَفُورًا ﴿٩٩﴾ ۞ وَمَن
يُهَاجِرْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ يَجِدْ فِى ٱلْأَرْضِ مُرَٰغَمًا كَثِيرًا وَسَعَةً ۚ وَمَن
يَخْرُجْ مِنۢ بَيْتِهِۦ مُهَاجِرًا إِلَى ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ثُمَّ يُدْرِكْهُ ٱلْمَوْتُ فَقَدْ
وَقَعَ أَجْرُهُۥ عَلَى ٱللَّهِ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿١٠٠﴾ وَإِذَا ضَرَبْتُمْ فِى
ٱلْأَرْضِ فَلَيْسَ عَلَيْكُمْ جُنَاحٌ أَن تَقْصُرُوا۟ مِنَ ٱلصَّلَوٰةِ إِنْ خِفْتُمْ
أَن يَفْتِنَكُمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ ۚ إِنَّ ٱلْكَٰفِرِينَ كَانُوا۟ لَكُمْ عَدُوًّا مُّبِينًا ﴿١٠١﴾

(95) Waɗanda suka zauna a gida daga cikin muminai ba su fita yaƙi ba, in dai ba masu larura ba, ba za su yi daidai da masu jihadi don ɗaukaka kalmar Allah da dukiyoyinsu da kawunansu ba. Allah Ya fifita darajar masu jihadi da dukiyoyinsu da kawunansu a kan waɗanda suka zauna a gida. Kuma dukkansu Allah Ya yi masu alƙawarin Aljanna. Kuma Allah Ya fifita masu jihadi a kan waɗanda suka zauna a gida, da lada mai girma (96) Wasu darajoji masu yawa daga gare Shi da gafara da kuma jin ƙai. Kuma Allah Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai (97) Lalle waɗanda mala'iku suke karɓar rayukansu suna masu zaluntar kawunansu[1], (mala'ikun) za su ce (da su): "Cikin wane hali kuka kasance?" Sai su ce: "Mu mun kasance masu rauni a bayan ƙasa." Sai su ce: "Ashe ƙasar Allah ba mai yalwa ba ce, ta yadda za ku sami damar yin hijira a cikinta?" To waɗannan, makomarsu ita ce wutar Jahannama, kuma wannan makoma ta munana (98) Sai dai waɗanda suke raunana cikin maza da mata da yara ƙanana waɗanda ba su da wata dabara, kuma ba za su gane wata hanya (ta hijira) ba[2] (99) To waɗannan mai yiwuwa ne Allah Ya yi musu afuwa, Allah kuma Ya kasance Mai afuwa ne, Mai yawan gafara (100) Kuma duk wanda ya yi hijira saboda Allah, zai samu wuraren hijira masu yawa da yalwa a bayan ƙasa. Kuma duk wanda ya fita daga gidansa, yana mai hijira zuwa ga Allah da Manzonsa, sannan mutuwa ta riske shi, to haƙiƙa ladansa ya tabbata a wajen Allah. Kuma Allah Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai (101) Kuma idan kun yi tafiya a bayan ƙasa, to babu laifi a kanku ku yi sallar ƙasaru[3], in kun ji tsoron kafirai su fitine ku[4]. Lalle kafirai sun kasance maƙiya ne, masu bayyana ƙiyayya a gare ku

(1) Watau sun ƙi yin hijira zuwa cikin 'yan'uwansu Musulmi, sun ci gaba da zama a ƙasar kafirci, tare da cewa suna da ikon yin hijirar.

(2) Watau ba su da wata hanya da za su kuɓutar da kansu daga hannun mushirikai.

(3) Watau ku taƙaita salloli masu raka'a huɗu zuwa raka'a biyu.

(4) Ko da yake an ambaci halin tsoron fitinar kafirai, to amma wannan ba sharaɗi ba ne, duk wanda yake a halin tafiya yana iya yin sallar ƙasaru.

وَإِذَا كُنتَ فِيهِمْ فَأَقَمْتَ لَهُمُ ٱلصَّلَوٰةَ فَلْتَقُمْ طَآئِفَةٌ
مِّنْهُم مَّعَكَ وَلْيَأْخُذُوٓاْ أَسْلِحَتَهُمْ ۖ فَإِذَا سَجَدُواْ فَلْيَكُونُواْ
مِن وَرَآئِكُمْ وَلْتَأْتِ طَآئِفَةٌ أُخْرَىٰ لَمْ يُصَلُّواْ فَلْيُصَلُّواْ
مَعَكَ وَلْيَأْخُذُواْ حِذْرَهُمْ وَأَسْلِحَتَهُمْ ۗ وَدَّ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ لَوْ تَغْفُلُونَ عَنْ أَسْلِحَتِكُمْ وَأَمْتِعَتِكُمْ فَيَمِيلُونَ
عَلَيْكُم مَّيْلَةً وَٰحِدَةً ۚ وَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ إِن كَانَ بِكُمْ
أَذًى مِّن مَّطَرٍ أَوْ كُنتُم مَّرْضَىٰٓ أَن تَضَعُوٓاْ أَسْلِحَتَكُمْ ۖ
وَخُذُواْ حِذْرَكُمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ أَعَدَّ لِلْكَٰفِرِينَ عَذَابًا مُّهِينًا ﴿١٠٢﴾
فَإِذَا قَضَيْتُمُ ٱلصَّلَوٰةَ فَٱذْكُرُواْ ٱللَّهَ قِيَٰمًا وَقُعُودًا وَعَلَىٰ
جُنُوبِكُمْ ۚ فَإِذَا ٱطْمَأْنَنتُمْ فَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ ۚ إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ
كَانَتْ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ كِتَٰبًا مَّوْقُوتًا ﴿١٠٣﴾ وَلَا تَهِنُواْ فِى
ٱبْتِغَآءِ ٱلْقَوْمِ ۖ إِن تَكُونُواْ تَأْلَمُونَ فَإِنَّهُمْ يَأْلَمُونَ كَمَا
تَأْلَمُونَ ۖ وَتَرْجُونَ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا يَرْجُونَ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ
عَلِيمًا حَكِيمًا ﴿١٠٤﴾ إِنَّآ أَنزَلْنَآ إِلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ بِٱلْحَقِّ لِتَحْكُمَ
بَيْنَ ٱلنَّاسِ بِمَآ أَرَىٰكَ ٱللَّهُ ۚ وَلَا تَكُن لِّلْخَآئِنِينَ خَصِيمًا ﴿١٠٥﴾

(102) Kuma idan ka kasance a cikinsu, sai ka yi musu limancin salla[1],, to sai wata ƙungiya su tsaya tare da kai, kuma su riƙe makamansu, to yayin da suka yi sujada (wato salla), sai su koma bayanku, sai ɗaya ƙungiyar wadda ba su yi salla ba, su zo su yi salla tare da kai, kuma su ma su yi taka-tsantsan, su kuma riƙe makamansu. Kafirai kuwa suna burin ina ma za ku gafala ku ajiye makamanku da kayayyakin guzurinku, sai su far muku gaba ɗaya. Kuma idan akwai wata cuta tare da ku saboda ruwan sama ko kun kasance marasa lafiya, to babu laifi a gare ku ku ajiye makamanku, amma fa ku yi taka-tsantsan. Lalle Allah Ya yi wa kafirai tanadin wata azaba mai wulaƙantarwa

(103) To idan kun kammala salla, to sai ku ambaci Allah a tsaye ko a zaune ko kuma a kwance. To idan kuka samu nutsuwa sai ku tsayar da salla (a yadda take). Lalle salla ta kasance wata farilla ce mai ƙayyadajjen lokaci a kan muminai


(104) Kuma kada ku yi rauni wajen neman mutanen; in kun kasance kuna jin raɗaɗi, to ai su ma (kafirai) suna jin raɗaɗi kamar yadda kuke jin raɗaɗi; kuma kuna fatan wani lada a wurin Allah, wanda su ba sa fatan irinsa. Allah kuwa Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai yawan hikima

(105) Lalle Mu Mun saukar maka da Littafi da gaskiya domin ka yi hukunci a tsakanin mutane da abin da Allah Ya sanar da kai, kuma kada ka zamo mai ba da kariya ga maha'inta

(1) Watau yadda zai yi wa sahabbansa limancin salla a lokacin da ake cikin halin yaƙi.

وَٱسْتَغْفِرِ ٱللَّهَ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿١٠٦﴾ وَلَا تُجَٰدِلْ
عَنِ ٱلَّذِينَ يَخْتَانُونَ أَنفُسَهُمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ مَن كَانَ
خَوَّانًا أَثِيمًا ﴿١٠٧﴾ يَسْتَخْفُونَ مِنَ ٱلنَّاسِ وَلَا يَسْتَخْفُونَ
مِنَ ٱللَّهِ وَهُوَ مَعَهُمْ إِذْ يُبَيِّتُونَ مَا لَا يَرْضَىٰ مِنَ ٱلْقَوْلِ ۚ
وَكَانَ ٱللَّهُ بِمَا يَعْمَلُونَ مُحِيطًا ﴿١٠٨﴾ هَٰٓأَنتُمْ هَٰٓؤُلَآءِ
جَٰدَلْتُمْ عَنْهُمْ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا فَمَن يُجَٰدِلُ ٱللَّهَ عَنْهُمْ
يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ أَم مَّن يَكُونُ عَلَيْهِ وَكِيلًا ﴿١٠٩﴾ وَمَن يَعْمَلْ
سُوٓءًا أَوْ يَظْلِمْ نَفْسَهُۥ ثُمَّ يَسْتَغْفِرِ ٱللَّهَ يَجِدِ ٱللَّهَ غَفُورًا
رَّحِيمًا ﴿١١٠﴾ وَمَن يَكْسِبْ إِثْمًا فَإِنَّمَا يَكْسِبُهُۥ عَلَىٰ نَفْسِهِۦ ۚ
وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمًا ﴿١١١﴾ وَمَن يَكْسِبْ خَطِيٓـَٔةً
أَوْ إِثْمًا ثُمَّ يَرْمِ بِهِۦ بَرِيٓـًٔا فَقَدِ ٱحْتَمَلَ بُهْتَٰنًا وَإِثْمًا مُّبِينًا
﴿١١٢﴾ وَلَوْلَا فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكَ وَرَحْمَتُهُۥ لَهَمَّت طَّآئِفَةٌ مِّنْهُمْ
أَن يُضِلُّوكَ وَمَا يُضِلُّونَ إِلَّآ أَنفُسَهُمْ ۖ وَمَا يَضُرُّونَكَ
مِن شَىْءٍ ۚ وَأَنزَلَ ٱللَّهُ عَلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ وَعَلَّمَكَ
مَا لَمْ تَكُن تَعْلَمُ ۚ وَكَانَ فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكَ عَظِيمًا ﴿١١٣﴾

(106) Kuma ka roƙi gafarar Allah, lalle Allah Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai
(107) Kuma kada ka kare waɗanda suke ha'intar kawunansu. Lalle Allah ba Ya son duk wanda ya kasance mai yawan ha'inci ne, mai yawan saɓo
(108) Suna ɓoye wa mutane (laifinsu), amma ba sa ɓoye wa Allah, alhali kuwa Yana tare da su yayin da suke kwana suna ƙulle-ƙullen maganar da bai yarda da ita ba. Kuma lalle Allah Ya kasance Mai kewayewa ne ga abin da suke aikatawa
(109) Sai ga shi ku waɗannan kun ba su kariya a rayuwar duniya, to wane ne zai ba su kariya a gaban Allah a ranar alƙiyama, ko kuwa wane ne zai zama wakilinsu?
(110) Kuma duk wanda ya aikata mummunan aiki ko ya zalunci kansa, sannan ya nemi gafarar Allah, to zai sami Allah Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai
(111) Kuma duk wanda ya aikata wani laifi, to kansa ya yi wa. Kuma Allah Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai hikima
(112) Kuma duk wanda ya aikata wani ƙaramin laifi, ko wani babban zunubi, sannan ya ɗora shi a kan wanda bai ji ba bai gani ba, to haƙiƙa ya ɗaukar wa kansa babban laifin ƙage da kuma wani zunubi mabayyani
(113) Ba don falalar Allah da rahamarsa a kanka ba kuwa, lalle da waɗansu jama'a daga cikinsu sun yi niyyar su ɓatar da kai, ba kuwa kowa za su iya ɓatarwa ba sai dai kawunansu; kuma ba za su cuce ka da komai ba. Kuma Allah Ya saukar maka da Littafi da hikima, kuma Ya sanar da kai abin da a da ba ka sani ba. Kuma falalar Allah mai girma ce gare ka



* لَّا خَيۡرَ فِي كَثِيرٖ مِّن نَّجۡوَىٰهُمۡ إِلَّا مَنۡ أَمَرَ بِصَدَقَةٍ
أَوۡ مَعۡرُوفٍ أَوۡ إِصۡلَٰحِۭ بَيۡنَ ٱلنَّاسِۚ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ
ٱبۡتِغَآءَ مَرۡضَاتِ ٱللَّهِ فَسَوۡفَ نُؤۡتِيهِ أَجۡرًا عَظِيمٗا ١١٤ وَمَن
يُشَاقِقِ ٱلرَّسُولَ مِنۢ بَعۡدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُ ٱلۡهُدَىٰ وَيَتَّبِعۡ غَيۡرَ
سَبِيلِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ نُوَلِّهِۦ مَا تَوَلَّىٰ وَنُصۡلِهِۦ جَهَنَّمَۖ وَسَآءَتۡ
مَصِيرًا ١١٥ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ
ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدۡ ضَلَّ ضَلَٰلَۢا
بَعِيدًا ١١٦ إِن يَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦٓ إِلَّآ إِنَٰثٗا وَإِن يَدۡعُونَ
إِلَّا شَيۡطَٰنٗا مَّرِيدٗا ١١٧ لَّعَنَهُ ٱللَّهُۘ وَقَالَ لَأَتَّخِذَنَّ مِنۡ
عِبَادِكَ نَصِيبٗا مَّفۡرُوضٗا ١١٨ وَلَأُضِلَّنَّهُمۡ وَلَأُمَنِّيَنَّهُمۡ
وَلَأٓمُرَنَّهُمۡ فَلَيُبَتِّكُنَّ ءَاذَانَ ٱلۡأَنۡعَٰمِ وَلَأٓمُرَنَّهُمۡ
فَلَيُغَيِّرُنَّ خَلۡقَ ٱللَّهِۚ وَمَن يَتَّخِذِ ٱلشَّيۡطَٰنَ وَلِيّٗا مِّن
دُونِ ٱللَّهِ فَقَدۡ خَسِرَ خُسۡرَانٗا مُّبِينٗا ١١٩ يَعِدُهُمۡ
وَيُمَنِّيهِمۡۖ وَمَا يَعِدُهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ إِلَّا غُرُورًا ١٢٠ أُوْلَٰٓئِكَ
مَأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُ وَلَا يَجِدُونَ عَنۡهَا مَحِيصٗا ١٢١

(114) Babu wani alheri a cikin yawancin ganawarsu, sai fa wanda ya yi umarni da yin sadaka, ko wani aiki nagari ko kuma sulhuntawa tsakanin mutane. Wanda ya aikata haka don neman yardar Allah, to za Mu ba shi lada mai girma

(115) Kuma duk wanda yake saba wa wannan Manzo bayan shiriya ta bayyana a gare shi, yake kuma bin tafarkin da ba na muminai ba, to za Mu bar shi da abin da ya ɗaukar wa kansa, sannan Mu shigar da shi wutar Jahannama; makoma kuwa ta munana

(116) Lalle Allah ba Ya gafartawa a yi masa shirka, Yana kuwa gafarta abin da bai kai shirka ba ga wanda Ya ga dama. Duk wanda ya yi wa Allah shirka, to haƙiƙa ya ɓata manisanciyar ɓata

(117) Ba waɗanda suke bauta wa, baya ga Allah, sai wasu gumaka masu sunan mata, kuma babu wanda suke bauta wa sai Shaiɗan mai taurin kai

(118) Allah Ya la'ance shi. Sai kuma ya ce: "Tabbas sai na samu wani kaso ƙayyadajje daga bayinka

(119) "Kuma lalle sai na ɓatar da su, kuma lalle sai na sa musu dogon buri, kuma lalle zan umarce su, sai sun riƙa gutsuttsure kunnuwan dabbobin gida, kuma lalle zan umarce su, sai sun canja halittar Allah." Duk wanda kuwa ya riƙi Shaiɗan a matsayin masoyi ba Allah ba, to haƙiƙa ya yi hasara bayyananniyar hasara

(120) Yana yi musu alƙawari kuma yana sa musu dogon buri; kuma babu abin da Shaiɗan yake yi musu alƙawari da shi sai ruɗi kawai

(121) Waɗannan makomarsu wutar Jahannama ce, kuma ba za su sami wurin kauce mata ba

وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَنُدۡخِلُهُمۡ جَنَّٰتٖ
تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۖ وَعۡدَ ٱللَّهِ
حَقّٗاۚ وَمَنۡ أَصۡدَقُ مِنَ ٱللَّهِ قِيلٗا ﴿١٢٢﴾ لَّيۡسَ بِأَمَانِيِّكُمۡ
وَلَآ أَمَانِيِّ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِۗ مَن يَعۡمَلۡ سُوٓءٗا يُجۡزَ بِهِۦ
وَلَا يَجِدۡ لَهُۥ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلِيّٗا وَلَا نَصِيرٗا ﴿١٢٣﴾ وَمَن
يَعۡمَلۡ مِنَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ
فَأُوْلَٰٓئِكَ يَدۡخُلُونَ ٱلۡجَنَّةَ وَلَا يُظۡلَمُونَ نَقِيرٗا ﴿١٢٤﴾ وَمَنۡ
أَحۡسَنُ دِينٗا مِّمَّنۡ أَسۡلَمَ وَجۡهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحۡسِنٞ وَٱتَّبَعَ
مِلَّةَ إِبۡرَٰهِيمَ حَنِيفٗاۗ وَٱتَّخَذَ ٱللَّهُ إِبۡرَٰهِيمَ خَلِيلٗا ﴿١٢٥﴾ وَلِلَّهِ
مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٖ
مُّحِيطٗا ﴿١٢٦﴾ وَيَسۡتَفۡتُونَكَ فِي ٱلنِّسَآءِۖ قُلِ ٱللَّهُ يُفۡتِيكُمۡ
فِيهِنَّ وَمَا يُتۡلَىٰ عَلَيۡكُمۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ فِي يَتَٰمَى ٱلنِّسَآءِ
ٱلَّٰتِي لَا تُؤۡتُونَهُنَّ مَا كُتِبَ لَهُنَّ وَتَرۡغَبُونَ أَن تَنكِحُوهُنَّ
وَٱلۡمُسۡتَضۡعَفِينَ مِنَ ٱلۡوِلۡدَٰنِ وَأَن تَقُومُواْ لِلۡيَتَٰمَىٰ بِٱلۡقِسۡطِۚ
وَمَا تَفۡعَلُواْ مِنۡ خَيۡرٖ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِهِۦ عَلِيمٗا ﴿١٢٧﴾

(122) Kuma waɗanda suka yi imani, kuma suka yi aiki nagari, za Mu shigar da su gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu har abada; kuma alƙawarin Allah tabbatacce ne. Kuma wane ne ya fi Allah gaskiyar zance?

(123) (Al'amarin) ba wai ya dangaci burace-buracenku ba ne, ba kuma burace-buracen Ma'abota Littafi ba ne. Duk wanda ya aikata mummunan aiki, to za a saka masa da shi, kuma ba zai sami wani masoyi ko mai taimako ba Allah ba

(124) Kuma wanda ya yi wani aiki nagari, namiji ne ko mace, alhali yana mumini, to waɗannan za su shiga Aljanna, kuma ba za a zalunce su gwargwadon ɗigon bayan ƙwallon dabino ba

(125) Kuma wane ne mafi kyawun addini fiye da wanda ya miƙa fuskarsa ga Allah, yana kuma mai kaɗaita Allah, sannan ya bi addinin Ibrahimu yana mai karkacewa duk wata ɓarna? Allah kuwa Ya riƙi Ibrahimu a matsayin badaɗayi

(126) Kuma abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa duk na Allah ne. Kuma Allah Ya kasance Yana kewaye da (sanin) komai

(127) Kuma suna neman fatawarka game da lamarin mata. Ka ce: "Allah ne Yake ba ku fatawa game da lamarinsu da kuma abin da ake karanta muku a cikin Littafi dangane da marayu mata waɗanda ba kwa iya ba su sadakinsu cikakke, ga shi kuma kuna kwaɗayin ku aure su; hakanan da kuma (dukiyar) yara masu rauni. Kuma ku tsaya wajen kula da (dukiyar) marayu ta hanyar adalci. Kuma duk abin da kuka aikata na alheri, to lalle Allah Yana sane da shi."

وَإِنِ ٱمۡرَأَةٌ خَافَتۡ مِنۢ بَعۡلِهَا نُشُوزًا أَوۡ إِعۡرَاضٗا فَلَا جُنَاحَ
عَلَيۡهِمَآ أَن يُصۡلِحَا بَيۡنَهُمَا صُلۡحٗاۚ وَٱلصُّلۡحُ خَيۡرٞۗ
وَأُحۡضِرَتِ ٱلۡأَنفُسُ ٱلشُّحَّۚ وَإِن تُحۡسِنُواْ وَتَتَّقُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ
كَانَ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٗا ١٢٨ وَلَن تَسۡتَطِيعُوٓاْ أَن تَعۡدِلُواْ
بَيۡنَ ٱلنِّسَآءِ وَلَوۡ حَرَصۡتُمۡۖ فَلَا تَمِيلُواْ كُلَّ ٱلۡمَيۡلِ فَتَذَرُوهَا
كَٱلۡمُعَلَّقَةِۚ وَإِن تُصۡلِحُواْ وَتَتَّقُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ
غَفُورٗا رَّحِيمٗا ١٢٩ وَإِن يَتَفَرَّقَا يُغۡنِ ٱللَّهُ كُلّٗا مِّن سَعَتِهِۦۚ
وَكَانَ ٱللَّهُ وَٰسِعًا حَكِيمٗا ١٣٠ وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ وَلَقَدۡ وَصَّيۡنَا ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ مِن
قَبۡلِكُمۡ وَإِيَّاكُمۡ أَنِ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ وَإِن تَكۡفُرُواْ فَإِنَّ لِلَّهِ
مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَنِيّٗا حَمِيدٗا
١٣١ وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلًا
١٣٢ إِن يَشَأۡ يُذۡهِبۡكُمۡ أَيُّهَا ٱلنَّاسُ وَيَأۡتِ بِـَٔاخَرِينَۚ وَكَانَ
ٱللَّهُ عَلَىٰ ذَٰلِكَ قَدِيرٗا ١٣٣ مَّن كَانَ يُرِيدُ ثَوَابَ ٱلدُّنۡيَا فَعِندَ ٱللَّهِ
ثَوَابُ ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ سَمِيعَۢا بَصِيرٗا ١٣٤

(128) Kuma idan wata mace ta ji tsoron burtsewa daga mijinta, ko bijirewa, to babu laifi su yi sulhu a tsakaninsu. Kuma yin sulhu shi ya fi alheri. Kuma an kimsa wa rayuka tsananin rowa. Idan kuka kyautata, kuma kuka yi takawa, to lalle Allah Ya kasance Masanin abin da kuke aikatawa ne

(129) Kuma ba za ku iya yin adalci (na soyayya) a tsakankanin mata ba, ko da kuna matukar son yin hakan. To kada ku karkata, karkata ta gaba ɗaya, ta yadda za ku kyale ɗayar kamar ratayayya[1]. Amma idan za ku kyautata kuma ku yi takawa, to lalle Allah Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin kai

(130) Idan kuwa suka rabu, to Allah zai wadatar da kowannensu daga yalwarsa. Kuma Allah Ya kasance Mayalwaci ne, Mai yawan hikima


(131) Kuma duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin kasa na Allah ne. Kuma hakika Mun yi wasiyya ga waɗanda Muka bai wa Littafi gabaninku da ku kanku cewa, ku ji tsoron Allah. Idan kuwa kuka kafirce, to lalle abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin kasa duka na Allah ne. Kuma Allah Ya kasance Mawadaci ne, Sha-yabo

(132) Kuma duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin kasa na Allah ne. kuma Allah Ya isa Abin dogaro

(133) Idan Ya ga dama sai Ya tafiyar da ku, ya ku mutane, kuma Ya kawo wadansu daban. Allah kuwa Ya kasance Mai iko ne a kan hakan

(134) Duk wanda ya kasance yana son ladan duniya, to ladan duniya da na lahira duk a hannun Allah suke. Kuma Allah Ya kasance Mai ji ne, Mai gani

(1) Watau su karkata ga ɗaya su kyale ɗayar a rataye, ita ba a sake ta ba ita kuma ba mai jin dadin aure ba.


يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُونُواْ قَوَّٰمِينَ بِٱلۡقِسۡطِ شُهَدَآءَ لِلَّهِ وَلَوۡ
عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمۡ أَوِ ٱلۡوَٰلِدَيۡنِ وَٱلۡأَقۡرَبِينَۚ إِن يَكُنۡ غَنِيًّا أَوۡ فَقِيرٗا
فَٱللَّهُ أَوۡلَىٰ بِهِمَاۖ فَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلۡهَوَىٰٓ أَن تَعۡدِلُواْۚ وَإِن تَلۡوُۥٓاْ
أَوۡ تُعۡرِضُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٗا ١٣٥ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلَّذِي نَزَّلَ
عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ مِن قَبۡلُۚ وَمَن يَكۡفُرۡ
بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ فَقَدۡ ضَلَّ
ضَلَٰلَۢا بَعِيدًا ١٣٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ثُمَّ كَفَرُواْ ثُمَّ ءَامَنُواْ ثُمَّ
كَفَرُواْ ثُمَّ ٱزۡدَادُواْ كُفۡرٗا لَّمۡ يَكُنِ ٱللَّهُ لِيَغۡفِرَ لَهُمۡ وَلَا لِيَهۡدِيَهُمۡ
سَبِيلَۢا ١٣٧ بَشِّرِ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ بِأَنَّ لَهُمۡ عَذَابًا أَلِيمًا ١٣٨ ٱلَّذِينَ
يَتَّخِذُونَ ٱلۡكَٰفِرِينَ أَوۡلِيَآءَ مِن دُونِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۚ أَيَبۡتَغُونَ
عِندَهُمُ ٱلۡعِزَّةَ فَإِنَّ ٱلۡعِزَّةَ لِلَّهِ جَمِيعٗا ١٣٩ وَقَدۡ نَزَّلَ عَلَيۡكُمۡ فِي
ٱلۡكِتَٰبِ أَنۡ إِذَا سَمِعۡتُمۡ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ يُكۡفَرُ بِهَا وَيُسۡتَهۡزَأُ بِهَا فَلَا
تَقۡعُدُواْ مَعَهُمۡ حَتَّىٰ يَخُوضُواْ فِي حَدِيثٍ غَيۡرِهِۦٓۚ إِنَّكُمۡ إِذٗا مِّثۡلُهُمۡۗ
إِنَّ ٱللَّهَ جَامِعُ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ وَٱلۡكَٰفِرِينَ فِي جَهَنَّمَ جَمِيعًا ١٤٠

(135) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku zamo masu tsayawa da adalci, kuna masu ba da shaida don Allah, ko da kuwa a kan kawunanku ne ko a kan mahaifanku ko a kan dangi makusanta. Idan ya kasance mawadaci ne ko matalauci, to Allah Shi ne Ya fi sanin abin da ya fi cancanta gare su[1]; don haka kada ku bi son zuciyarku ku ƙi yin adalci. Idan kuwa kuka karkatar da shaida ko kuka ƙi ba da ita, to lalle Allah Ya kasance Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne

(136) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi imani[2] da Allah da Manzonsa da Littafin da Ya saukar ga Manzonsa da Littafin da Ya saukar gabaninsa. Duk wanda kuwa ya kafirce wa Allah da mala'ikunsa da littattafansa da manzanninsa da ranar ƙarshe, to haƙiƙa ya ɓace ɓata mai nisa

(137) Lalle waɗanda suka yi imani, sannan daga baya suka kafirce, sannan kuma suka ƙara yin imani, sannan suka kafirce, sannan suka ƙara kafirci, waɗannan Allah ba zai yi musu gafara ba, ba kuma zai shiryar da su tafarki madaidaici ba

(138) Ka yi albishir ga munafukai cewa, suna da wata azaba mai raɗaɗi

(139) Su ne waɗanda suke rikar kafirai a matsayin masoya, su ƙyale muminai. Shin suna neman wata ɗaukaka ce a wurinsu? To lalle ɗaukaka gaba ɗaya ta Allah ce[3]

(140) Kuma haƙiƙa Ya saukar muku a cikin littafi[4] cewa, idan kuka ji ayoyin Allah ana kafirce musu, ana izgili da su, to kar ku zauna tare da su har sai sun shiga cikin wani zancen daban ba wannan ba. Lalle in har kuka zauna tare da su, to kun zama kamarsu. Lalle Allah Mai tattara munafukai ne da kafirai cikin wutar Jahannama gaba ɗaya

(1) Watau da mai wadata da matalauci duk al'amuransu na ga Allah, ya fi kowa sanin abin da ya fi zama maslaha a gare su.

(2) Watau ku tsaya ƙyam a kan imaninsu da Allah da Annabinsa ( ), su rike addininsu da kyau.

(3) Watau shi ne yake bayar da girma, kuma ga muminai kaɗai yake ba da shi, don haka munafukai ba za su same shi ba.

(4) Watau a cikin Alƙur'ani a Suratul An'am, aya ta 68 inda Allah ya haramta wa muminai zama a inda ake yi wa shari'ar Allah izgili da rashin kunya.

ٱلَّذِينَ يَتَرَبَّصُونَ بِكُمْ فَإِن كَانَ لَكُمْ فَتْحٌ مِّنَ ٱللَّهِ قَالُوٓا۟
أَلَمْ نَكُن مَّعَكُمْ وَإِن كَانَ لِلْكَٰفِرِينَ نَصِيبٌ قَالُوٓا۟
أَلَمْ نَسْتَحْوِذْ عَلَيْكُمْ وَنَمْنَعْكُم مِّنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ۚ فَٱللَّهُ يَحْكُمُ
بَيْنَكُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۗ وَلَن يَجْعَلَ ٱللَّهُ لِلْكَٰفِرِينَ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ
سَبِيلًا ﴿١٤١﴾ إِنَّ ٱلْمُنَٰفِقِينَ يُخَٰدِعُونَ ٱللَّهَ وَهُوَ خَٰدِعُهُمْ وَإِذَا
قَامُوٓا۟ إِلَى ٱلصَّلَوٰةِ قَامُوا۟ كُسَالَىٰ يُرَآءُونَ ٱلنَّاسَ وَلَا يَذْكُرُونَ
ٱللَّهَ إِلَّا قَلِيلًا ﴿١٤٢﴾ مُّذَبْذَبِينَ بَيْنَ ذَٰلِكَ لَآ إِلَىٰ هَٰٓؤُلَآءِ وَلَآ إِلَىٰ
هَٰٓؤُلَآءِ ۚ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ سَبِيلًا ﴿١٤٣﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ لَا تَتَّخِذُوا۟ ٱلْكَٰفِرِينَ أَوْلِيَآءَ مِن دُونِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ۚ
أَتُرِيدُونَ أَن تَجْعَلُوا۟ لِلَّهِ عَلَيْكُمْ سُلْطَٰنًا مُّبِينًا ﴿١٤٤﴾ إِنَّ
ٱلْمُنَٰفِقِينَ فِى ٱلدَّرْكِ ٱلْأَسْفَلِ مِنَ ٱلنَّارِ وَلَن تَجِدَ لَهُمْ نَصِيرًا
﴿١٤٥﴾ إِلَّا ٱلَّذِينَ تَابُوا۟ وَأَصْلَحُوا۟ وَٱعْتَصَمُوا۟ بِٱللَّهِ وَأَخْلَصُوا۟
دِينَهُمْ لِلَّهِ فَأُو۟لَٰٓئِكَ مَعَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ۖ وَسَوْفَ يُؤْتِ ٱللَّهُ
ٱلْمُؤْمِنِينَ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿١٤٦﴾ مَّا يَفْعَلُ ٱللَّهُ بِعَذَابِكُمْ
إِن شَكَرْتُمْ وَءَامَنتُمْ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ شَاكِرًا عَلِيمًا ﴿١٤٧﴾

(141) Su ne waɗanda suke fakon ku, idan kun sami wata nasara daga Allah sai su ce: "Shin ashe ba tare da ku muke ba?" Kuma idan kafirai ne suka samu wata nasara, sai su ce: "Ashe ba mu muka sami dama a kanku ba (amma muka ƙyale ku), kuma muka kare ku daga muminai?" To lalle Allah zai yi hukunci a tsakaninku ranar alƙiyama, kuma Allah ba zai taɓa ba wa kafirai wata dama ba a kan muminai[1]

(142) Lalle munafukai suna yaudarar Allah, alhali kuwa Shi Mai mayar musu da sakamakon yaudararsu ne; kuma idan sun tashi zuwa salla, za su tashi suna masu kasala ne, suna yin aiki don mutane su gani, kuma ba su ambaton Allah sai kaɗan

(143) Suna ta kai-kawo tsakanin haka (kafirci da imani), su ba sa tare da waɗanan, kuma ba sa tare da waɗancan. Duk wanda Allah Ya ɓatar da shi kuwa, to babu yadda za ka iya sama masa wani tafarki na shiriya

(144) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku riƙi kafirai a matsayin masoya ku bar muminai. Shin kuna so ku ba wa Allah wata hujja mabayyaniya ne a kanku?

(145) Lalle munafukai suna cikin matakin ƙarshe na can ƙarƙashin wuta, kuma ba za ka taɓa sama musu wani mataimaki ba

(146) Sai fa waɗanda suka tuba, kuma suka gyara aikinsu, kuma suka yi riƙo ga igiyar Allah; kuma suka tsantsanta addininsu don Allah; to waɗannan suna tare da muminai; kuma Allah zai bai wa muminai lada mai girma

(147) Me Allah zai yi da azabtar da ku idan har kun yi godiya kuma kun yi imani? Allah kuwa Ya kasance Mai godiya ne, Mai yawan sani

(1) Watau ba zai taɓa ba su nasara a kan muminai gaba ɗaya ba, sai dai ta wani wuri ban da wani wuri. Hakanan a lahira ba zai ba su hujjar da za su rinjayi muminai da ita ba.

لَّا يُحِبُّ ٱللَّهُ ٱلْجَهْرَ بِٱلسُّوٓءِ مِنَ ٱلْقَوْلِ إِلَّا مَن ظُلِمَ ۚ وَكَانَ
ٱللَّهُ سَمِيعًا عَلِيمًا ﴿١٤٨﴾ إِن تُبْدُوا۟ خَيْرًا أَوْ تُخْفُوهُ أَوْ تَعْفُوا۟ عَن
سُوٓءٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَفُوًّا قَدِيرًا ﴿١٤٩﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكْفُرُونَ
بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ وَيُرِيدُونَ أَن يُفَرِّقُوا۟ بَيْنَ ٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ وَيَقُولُونَ
نُؤْمِنُ بِبَعْضٍ وَنَكْفُرُ بِبَعْضٍ وَيُرِيدُونَ أَن يَتَّخِذُوا۟
بَيْنَ ذَٰلِكَ سَبِيلًا ﴿١٥٠﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْكَٰفِرُونَ حَقًّا ۚ وَأَعْتَدْنَا
لِلْكَٰفِرِينَ عَذَابًا مُّهِينًا ﴿١٥١﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ
وَلَمْ يُفَرِّقُوا۟ بَيْنَ أَحَدٍ مِّنْهُمْ أُو۟لَٰٓئِكَ سَوْفَ يُؤْتِيهِمْ
أُجُورَهُمْ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿١٥٢﴾ يَسْـَٔلُكَ أَهْلُ ٱلْكِتَٰبِ
أَن تُنَزِّلَ عَلَيْهِمْ كِتَٰبًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ ۚ فَقَدْ سَأَلُوا۟ مُوسَىٰٓ أَكْبَرَ
مِن ذَٰلِكَ فَقَالُوٓا۟ أَرِنَا ٱللَّهَ جَهْرَةً فَأَخَذَتْهُمُ ٱلصَّٰعِقَةُ بِظُلْمِهِمْ ۚ
ثُمَّ ٱتَّخَذُوا۟ ٱلْعِجْلَ مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَتْهُمُ ٱلْبَيِّنَٰتُ فَعَفَوْنَا
عَن ذَٰلِكَ ۚ وَءَاتَيْنَا مُوسَىٰ سُلْطَٰنًا مُّبِينًا ﴿١٥٣﴾ وَرَفَعْنَا فَوْقَهُمُ
ٱلطُّورَ بِمِيثَٰقِهِمْ وَقُلْنَا لَهُمُ ٱدْخُلُوا۟ ٱلْبَابَ سُجَّدًا وَقُلْنَا
لَهُمْ لَا تَعْدُوا۟ فِى ٱلسَّبْتِ وَأَخَذْنَا مِنْهُم مِّيثَٰقًا غَلِيظًا ﴿١٥٤﴾

(148) Allah ba Ya son bayyana mummunan zance, sai dai wanda aka zalunce shi. Kuma Allah Ya kasance Mai ji ne, Mai yawan sani

(149) Idan har kuka bayyana wani alheri ko kuka ɓoye shi ko kuma kuka yi afuwa game da wata cutarwa, to lalle Allah Ya kasance Mai yawan afuwa ne, Mai cikakken iko

(150) Lalle waɗanda suke kafirce wa Allah da manzanninsa, kuma suke nufin su nuna bambanci tsakanin Allah da manzanninsa, kuma suna cewa: "Mun yi imani da wasu, mun kuma kafirce wa wasu," kuma suna son su riƙi wani tafarki tsakanin wannan (imani da kafirci)

(151) Waɗannan su ne kafirai na haƙiƙa. Kuma Mun yi wa kafirai tanadin wata azaba mai wulaƙantarwa

(152) Waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa, kuma ba su nuna bambanci tsakanin ɗaya daga cikinsu ba, waɗannan (Allah) zai ba su ladansu. Allah kuma Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai yawan rahama

(153) Ma'abota Littafi (Yahudawa da Nasara) suna tambayar ka cewa, ka saukar musu da wani cikakken littafi daga sama. To haƙiƙa da ma can sun tambayi Musa abin da ya fi wannan girma, da suka ce: "Ka nuna mana Allah a fili," sai tsawa ta far musu a sanadiyyar zaluncinsu. Sannan kuma suka riƙi ɗan maraƙi abin bauta bayan hujjoji sun zo musu, sai Muka yi (musu) afuwa a kan haka. Kuma Muka bai wa Musa hujja bayyananniya

(154) Kuma Muka ɗaga dutsen Ɗuri a kansu don su karɓi alƙawarinsu, kuma Muka ce da su: "Ku shiga ƙofar (garin) a sunkuye." Kuma Muka ce da su: "Kada ku ƙetare iyaka (ta kamun kifi) a ranar Asabar," kuma Muka yi alƙawari mai ƙarfi da su

فَبِمَا نَقْضِهِم مِّيثَٰقَهُمْ وَكُفْرِهِم بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَقَتْلِهِمُ ٱلْأَنۢبِيَآءَ
بِغَيْرِ حَقٍّ وَقَوْلِهِمْ قُلُوبُنَا غُلْفٌۢ ۚ بَلْ طَبَعَ ٱللَّهُ عَلَيْهَا بِكُفْرِهِمْ
فَلَا يُؤْمِنُونَ إِلَّا قَلِيلًا ﴿١٥٥﴾ وَبِكُفْرِهِمْ وَقَوْلِهِمْ عَلَىٰ مَرْيَمَ بُهْتَٰنًا
عَظِيمًا ﴿١٥٦﴾ وَقَوْلِهِمْ إِنَّا قَتَلْنَا ٱلْمَسِيحَ عِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ رَسُولَ
ٱللَّهِ وَمَا قَتَلُوهُ وَمَا صَلَبُوهُ وَلَٰكِن شُبِّهَ لَهُمْ ۚ وَإِنَّ ٱلَّذِينَ
ٱخْتَلَفُوا۟ فِيهِ لَفِى شَكٍّ مِّنْهُ ۚ مَا لَهُم بِهِۦ مِنْ عِلْمٍ إِلَّا ٱتِّبَاعَ ٱلظَّنِّ ۚ
وَمَا قَتَلُوهُ يَقِينًۢا ﴿١٥٧﴾ بَل رَّفَعَهُ ٱللَّهُ إِلَيْهِ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا
﴿١٥٨﴾ وَإِن مِّنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ إِلَّا لَيُؤْمِنَنَّ بِهِۦ قَبْلَ مَوْتِهِۦ ۖ وَيَوْمَ
ٱلْقِيَٰمَةِ يَكُونُ عَلَيْهِمْ شَهِيدًا ﴿١٥٩﴾ فَبِظُلْمٍ مِّنَ ٱلَّذِينَ هَادُوا۟
حَرَّمْنَا عَلَيْهِمْ طَيِّبَٰتٍ أُحِلَّتْ لَهُمْ وَبِصَدِّهِمْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ
كَثِيرًا ﴿١٦٠﴾ وَأَخْذِهِمُ ٱلرِّبَوٰا۟ وَقَدْ نُهُوا۟ عَنْهُ وَأَكْلِهِمْ أَمْوَٰلَ
ٱلنَّاسِ بِٱلْبَٰطِلِ ۚ وَأَعْتَدْنَا لِلْكَٰفِرِينَ مِنْهُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿١٦١﴾ لَّٰكِنِ
ٱلرَّٰسِخُونَ فِى ٱلْعِلْمِ مِنْهُمْ وَٱلْمُؤْمِنُونَ يُؤْمِنُونَ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيْكَ
وَمَآ أُنزِلَ مِن قَبْلِكَ وَٱلْمُقِيمِينَ ٱلصَّلَوٰةَ وَٱلْمُؤْتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ
وَٱلْمُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ سَنُؤْتِيهِمْ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿١٦٢﴾



(155) To saboda warware alkawarinsu da kafircewarsu ga ayoyin Allah da kuma kashe wasu annabawan ba tare da wani laifi ba da kuma fadinsu cewa: "Zukatanmu a rufe suke."A'a, ba haka ne ba, Allah ne Ya rufe su saboda kafircinsu, don haka ba za su yi imani ba sai dan kadan
(156) Kuma saboda kafircinsu da kuma wata babbar karya da suka yi wa Maryamu[1]
(157) Da kuma fadarsu cewa: "Lalle mu mun kashe Almasihu Isa dan Maryamu Manzon Allah," alhalin kuwa ba su kashe shi ba, kuma ba su gicciye shi ba, sai dai an kamanta musu (wani da shi ne)[2]. Kuma lalle wadanda suka yi sabani game da shi (Annabi Isa) suna cikin shakka game da (kashe) shi, ba su da wani ilimi face bin zato. Kuma a hakikanin gaskiya ba su kashe shi ba
(158) Ba haka ba ne, Allah ya daga shi zuwa gare Shi ne. kuma Allah Ya kasance Mabuwayi ne, Mai hikima
(159) Kuma babu wani daga Ma'abota Littafi face sai ya yi imani da shi kafin mutuwarsa[3]; kuma a ranar tashin alkiyama zai zama mai ba da shaida a kansu
(160) To saboda zaluncin wadanda suka zama Yahudawa, Muka haramta musu dadadan abubuwan da aka halatta musu, kuma saboda suna yawan hana mutane bin hanyar Allah
(161) Da kuma cin riba da suke yi, tare da cewa an hana su cin ta, da kuma yadda suke cin dukiyar mutane ta hanyar cuta, Mun kuwa yi tanadin azaba mai radadi ga kafirai daga cikinsu
(162) Amma masu zurfin ilimi daga cikinsu da muminai, suna imani da abin da aka saukar maka da abin da aka saukar gabaninka; musamman ma masu tsayar da salla, da kuma masu bayar da zakka, kuma masu imani da Allah da ranar karshe. Wadannan ba da jimawa ba za Mu ba su lada mai girma

(1) Watau tuhumar da Yahudawa suka yi mata da cewa, wai zina ta yi ta haifi Annabi Isa ( ).

(2) Watau suka zaci shi ne Annabi Isa ( ), suka kama shi suka kashe.

(3) Watau lokacin da Annabi Isa ( ) zai sauko kasa a karshen zamani duk wani Bayahude ba Banasare sai ya yi imani da shi kafin mutuwar Annabi Isa ( ).



إِنَّآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ كَمَآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ نُوحٖ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ مِنۢ بَعۡدِهِۦۚ
وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ
وَٱلۡأَسۡبَاطِ وَعِيسَىٰ وَأَيُّوبَ وَيُونُسَ وَهَٰرُونَ وَسُلَيۡمَٰنَۚ
وَءَاتَيۡنَا دَاوُۥدَ زَبُورٗا ١٦٣ وَرُسُلٗا قَدۡ قَصَصۡنَٰهُمۡ عَلَيۡكَ
مِن قَبۡلُ وَرُسُلٗا لَّمۡ نَقۡصُصۡهُمۡ عَلَيۡكَۚ وَكَلَّمَ ٱللَّهُ مُوسَىٰ
تَكۡلِيمٗا ١٦٤ رُّسُلٗا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ
لِلنَّاسِ عَلَى ٱللَّهِ حُجَّةُۢ بَعۡدَ ٱلرُّسُلِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمٗا
١٦٥ لَّٰكِنِ ٱللَّهُ يَشۡهَدُ بِمَآ أَنزَلَ إِلَيۡكَۖ أَنزَلَهُۥ بِعِلۡمِهِۦۖ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ
يَشۡهَدُونَۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدًا ١٦٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
وَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ قَدۡ ضَلُّواْ ضَلَٰلَۢا بَعِيدًا ١٦٧ إِنَّ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ وَظَلَمُواْ لَمۡ يَكُنِ ٱللَّهُ لِيَغۡفِرَ لَهُمۡ وَلَا لِيَهۡدِيَهُمۡ
طَرِيقًا ١٦٨ إِلَّا طَرِيقَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۚ وَكَانَ
ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٗا ١٦٩ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدۡ جَآءَكُمُ ٱلرَّسُولُ بِٱلۡحَقِّ
مِن رَّبِّكُمۡ فَـَٔامِنُواْ خَيۡرٗا لَّكُمۡۚ وَإِن تَكۡفُرُواْ فَإِنَّ لِلَّهِ
مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمٗا ١٧٠

(163) Lalle Mun yi maka wahayi irin wahayin da Muka yi wa Nuhu da kuma annabawan da suka biyo bayansa, kuma Mun yi wahayi ga Ibrahimu da Isma'ila da Ishaƙa da Ya'aƙubu da kuma jikokin (Ya'aƙubu) da Isa da Ayyuba da Yunusa da Haruna da Sulaimanu; kuma Muka bai wa Dawuda littafin Zabura
(164) (Muka) kuma aiko manzanni waɗanda Muka ba ka labarinsu tun da farko, da waɗansu manzannin daban da ba Mu ba ka labarinsu ba; kuma Allah Ya yi magana da Musa kai-tsaye
(165) Manzanni ne masu albishir kuma masu gargaɗi, domin kada mutane su sami wata hujja a wurin Allah bayan aiko manzannin. Kuma Allah Ya kasance Mabuwayi ne, Mai hikima
(166) Amma Allah Yana shaida game da abin da Ya saukar maka; Ya saukar da shi ne da iliminsa; haka mala'iku ma suna shaidawa. Kuma Allah Ya isa Mai shaida
(167) Lalle waɗanda suka kafirta, kuma suka kange mutane daga hanyar Allah, haƙiƙa sun ɓace ɓata mai nisa
(168) Lalle waɗanda suka kafirta, kuma suka yi zalunci, Allah ba zai taɓa yi musu gafara ba, ba kuma zai shiryar da su wata hanya ta gari ba
(169) Sai dai hanyar wutar Jahannama, suna masu dawwama a cikinta har abada. Yin hakan kuwa ya kasance abu ne mai sauƙi a wajen Allah
(170) Ya ku mutane, haƙiƙa Manzo ya zo muku da gaskiya daga wajen Ubangijinku, don haka ku yi imani shi ya fi alheri a gare ku. Idan kuwa kuka kafirce, to lalle abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa duk na Allah ne. kuma Allah Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai hikima

يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ لَا تَغۡلُواْ فِي دِينِكُمۡ وَلَا تَقُولُواْ عَلَى
ٱللَّهِ إِلَّا ٱلۡحَقَّۚ إِنَّمَا ٱلۡمَسِيحُ عِيسَى ٱبۡنُ مَرۡيَمَ رَسُولُ ٱللَّهِ
وَكَلِمَتُهُۥٓ أَلۡقَىٰهَآ إِلَىٰ مَرۡيَمَ وَرُوحٞ مِّنۡهُۖ فَـَٔامِنُواْ بِٱللَّهِ
وَرُسُلِهِۦۖ وَلَا تَقُولُواْ ثَلَٰثَةٌۚ ٱنتَهُواْ خَيۡرٗا لَّكُمۡۚ إِنَّمَا ٱللَّهُ
إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۖ سُبۡحَانَهُۥٓ أَن يَكُونَ لَهُۥ وَلَدٞۘ لَّهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلٗا ١٧١ لَّن يَسۡتَنكِفَ
ٱلۡمَسِيحُ أَن يَكُونَ عَبۡدٗا لِّلَّهِ وَلَا ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ ٱلۡمُقَرَّبُونَۚ
وَمَن يَسۡتَنكِفۡ عَنۡ عِبَادَتِهِۦ وَيَسۡتَكۡبِرۡ فَسَيَحۡشُرُهُمۡ
إِلَيۡهِ جَمِيعٗا ١٧٢ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
فَيُوَفِّيهِمۡ أُجُورَهُمۡ وَيَزِيدُهُم مِّن فَضۡلِهِۦۖ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ
ٱسۡتَنكَفُواْ وَٱسۡتَكۡبَرُواْ فَيُعَذِّبُهُمۡ عَذَابًا أَلِيمٗا وَلَا
يَجِدُونَ لَهُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ وَلِيّٗا وَلَا نَصِيرٗا ١٧٣ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ
قَدۡ جَآءَكُم بُرۡهَٰنٞ مِّن رَّبِّكُمۡ وَأَنزَلۡنَآ إِلَيۡكُمۡ نُورٗا مُّبِينٗا
١٧٤ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَٱعۡتَصَمُواْ بِهِۦ فَسَيُدۡخِلُهُمۡ فِي
رَحۡمَةٖ مِّنۡهُ وَفَضۡلٖ وَيَهۡدِيهِمۡ إِلَيۡهِ صِرَٰطٗا مُّسۡتَقِيمٗا ١٧٥

(171) Ya ku Ma'abota Littafi, kada ku wuce iyaka cikin addininku[1], kuma kada ku fadi wata magana game da Allah sai ta gaskiya. Almasihu Isa ɗan Maryamu Manzon Allah ne, kuma kalmarsa ce da ya jefa wa Maryamu, kuma Ruhi ne daga gare Shi; don haka ku yi imani da Allah da manzanninsa, kuma kada ku rika cewa su uku ne. Ku daina shi ya fi alheri a gare ku. Allah Shi ne kaɗai abin bauta da gaskiya, Daya ne; Ya tsarkaka a ce Yana da ɗa. Kuma abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nasa ne, kuma Allah Ya isa Abin dogaro

(172) Almasihu ba zai taɓa ƙyamar ya zama bawan Allah ba, hakanan su ma mala'iku makusanta. Duk wanda yake ƙyamar bautar Allah, kuma suke girman kai, to zai tattara su gaba ɗaya zuwa gare Shi

(173) To amma waɗanda suka yi imani, kuma suka yi ayyuka nagari, to zai cika musu ladansu, kuma Ya ƙara musu daga falalarsa. Amma waɗanda suka ƙyamaci bautar Allah kuwa, suka kuma yi girman kai, to zai azabtar da su azaba mai raɗaɗi, kuma ba za su taɓa samun wani masoyi ko mataimaki ba Allah ba

(174) Ya ku mutane, haƙiƙa hujja ta zo muku daga Ubangijinku, kuma Mun saukar muku wani haske mabayyani[2]

(175) To amma waɗanda suka yi imani da Allah kuma suka yi garkuwa da Shi, to zai shigar da su cikin wata rahama tasa da kuma wata falala, kuma Ya shiryar da su tafarki madaidaici zuwa gare Shi

(1) Watau kada su wuce iyaka wajen kuzuzuta lamarin Annabi Isa ( ) har ta kai su ga cewa ɗan Allah ne.

(2) Watau Alƙur'ani mai girma.

يَسْتَفْتُونَكَ قُلِ ٱللَّهُ يُفْتِيكُمْ فِى ٱلْكَلَٰلَةِ ۚ إِنِ ٱمْرُؤٌا۟ هَلَكَ
لَيْسَ لَهُۥ وَلَدٌ وَلَهُۥٓ أُخْتٌ فَلَهَا نِصْفُ مَا تَرَكَ ۚ وَهُوَ يَرِثُهَآ إِن
لَّمْ يَكُن لَّهَا وَلَدٌ ۚ فَإِن كَانَتَا ٱثْنَتَيْنِ فَلَهُمَا ٱلثُّلُثَانِ مِمَّا تَرَكَ ۚ
وَإِن كَانُوٓا۟ إِخْوَةً رِّجَالًا وَنِسَآءً فَلِلذَّكَرِ مِثْلُ حَظِّ ٱلْأُنثَيَيْنِ ۗ
يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمْ أَن تَضِلُّوا۟ ۗ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌۢ ﴿١٧٦﴾

سُورَةُ المَائِدَة

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَوْفُوا۟ بِٱلْعُقُودِ ۚ أُحِلَّتْ لَكُم بَهِيمَةُ ٱلْأَنْعَٰمِ
إِلَّا مَا يُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ غَيْرَ مُحِلِّى ٱلصَّيْدِ وَأَنتُمْ حُرُمٌ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ
يَحْكُمُ مَا يُرِيدُ ﴿١﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تُحِلُّوا۟ شَعَٰٓئِرَ ٱللَّهِ
وَلَا ٱلشَّهْرَ ٱلْحَرَامَ وَلَا ٱلْهَدْىَ وَلَا ٱلْقَلَٰٓئِدَ وَلَآ ءَآمِّينَ ٱلْبَيْتَ
ٱلْحَرَامَ يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّن رَّبِّهِمْ وَرِضْوَٰنًا ۚ وَإِذَا حَلَلْتُمْ فَٱصْطَادُوا۟ ۚ
وَلَا يَجْرِمَنَّكُمْ شَنَـَٔانُ قَوْمٍ أَن صَدُّوكُمْ عَنِ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ أَن
تَعْتَدُوا۟ ۘ وَتَعَاوَنُوا۟ عَلَى ٱلْبِرِّ وَٱلتَّقْوَىٰ ۖ وَلَا تَعَاوَنُوا۟ عَلَى ٱلْإِثْمِ
وَٱلْعُدْوَٰنِ ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿٢﴾

(176) Suna neman ka yi musu fatawa, ka ce: “Allah ne zai yi muku fatawa game da kalala. Idan mutum ya mutu ba shi da ɗa ko ‘ya, amma yana da ‘yar’uwa mace, to za a ba ta rabin abin da ya bari. Shi kuwa zai gaje (dukiyar) ta gaba ɗaya idan ya kasance ba ta da ɗa ko ‘ya. Amma idan suka kasance mata ne su biyu, to suna da biyu bisa uku na abin da ya bari. Idan kuwa sun kasance ‘yan’uwa masu yawa maza da mata, to duk namiji ɗaya yana da rabon mata biyu.” Allah Yana bayyana muku wannan ne don kar ku ɓace. Kuma Allah Masanin komai ne

Sura Ma’ida

(1) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku cika alƙawura. An halatta muku dabbobin ni’ima, sai dai abin da ake karanta muku (haramcinsa), ba kuna masu halatta farauta ba alhalin kuna cikin Harami, lalle Allah Yana hukunta abin da Yake nufi

(2) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku halatta keta alfarmar alamomin addinin Allah, ko (ku wulaƙanta) Wata mai alfarma[1] ko dabbobin hadaya ko dabbobin hadaya masu alama da (tare) masu nufin ziyarar Ɗaki mai alfarma, suna neman falala daga wurin Ubangijinsu da yardarsa. Idan kuwa kuka kwance Harami, to ku yi farauta (idan kuna so). Kuma kada ƙiyayyar wasu mutane da suka hana ku isa masallaci mai alfarma, ta sa ku yi ta’addanci. Kuma ku taimaki juna a kan aikin alheri da taƙawa; kada kuma ku taimaka wa juna a kan ayyukan saɓo da ta’addanci. Kuma ku kiyaye dokokin Allah; lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne

(1) Watanni masu alfarma su ne: Zulƙi’ida, Zulhijja, Al-Muharram da Rajab. An haramta yaƙi a cikinsu.

حُرِّمَتْ عَلَيْكُمُ ٱلْمَيْتَةُ وَٱلدَّمُ وَلَحْمُ ٱلْخِنزِيرِ وَمَآ أُهِلَّ لِغَيْرِ ٱللَّهِ بِهِۦ
وَٱلْمُنْخَنِقَةُ وَٱلْمَوْقُوذَةُ وَٱلْمُتَرَدِّيَةُ وَٱلنَّطِيحَةُ وَمَآ أَكَلَ
ٱلسَّبُعُ إِلَّا مَا ذَكَّيْتُمْ وَمَا ذُبِحَ عَلَى ٱلنُّصُبِ وَأَن تَسْتَقْسِمُوا۟
بِٱلْأَزْلَٰمِ ۚ ذَٰلِكُمْ فِسْقٌ ۗ ٱلْيَوْمَ يَئِسَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِن دِينِكُمْ فَلَا
تَخْشَوْهُمْ وَٱخْشَوْنِ ۚ ٱلْيَوْمَ أَكْمَلْتُ لَكُمْ دِينَكُمْ وَأَتْمَمْتُ عَلَيْكُمْ
نِعْمَتِى وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلْإِسْلَٰمَ دِينًا ۚ فَمَنِ ٱضْطُرَّ فِى مَخْمَصَةٍ
غَيْرَ مُتَجَانِفٍ لِّإِثْمٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٣﴾ يَسْـَٔلُونَكَ مَاذَآ
أُحِلَّ لَهُمْ ۖ قُلْ أُحِلَّ لَكُمُ ٱلطَّيِّبَٰتُ وَمَا عَلَّمْتُم مِّنَ ٱلْجَوَارِحِ
مُكَلِّبِينَ تُعَلِّمُونَهُنَّ مِمَّا عَلَّمَكُمُ ٱللَّهُ ۖ فَكُلُوا۟ مِمَّآ أَمْسَكْنَ عَلَيْكُمْ
وَٱذْكُرُوا۟ ٱسْمَ ٱللَّهِ عَلَيْهِ ۖ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلْحِسَابِ ﴿٤﴾
ٱلْيَوْمَ أُحِلَّ لَكُمُ ٱلطَّيِّبَٰتُ ۖ وَطَعَامُ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ حِلٌّ لَّكُمْ
وَطَعَامُكُمْ حِلٌّ لَّهُمْ ۖ وَٱلْمُحْصَنَٰتُ مِنَ ٱلْمُؤْمِنَٰتِ وَٱلْمُحْصَنَٰتُ
مِنَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ مِن قَبْلِكُمْ إِذَآ ءَاتَيْتُمُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ
مُحْصِنِينَ غَيْرَ مُسَٰفِحِينَ وَلَا مُتَّخِذِىٓ أَخْدَانٍ ۗ وَمَن يَكْفُرْ
بِٱلْإِيمَٰنِ فَقَدْ حَبِطَ عَمَلُهُۥ وَهُوَ فِى ٱلْءَاخِرَةِ مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿٥﴾

(3) An haramta muku (cin) mushe da jini da naman alade da abin da aka yanka shi da sunan wanin Allah, da (dabbar) da ta shaƙe, da wadda aka doke ta, da wadda ta gangaro (daga sama), da dabbar da aka tunkura da ƙaho, da kuma abin da namun daji masu farauta suka ci, sai dai abin da kuka samu damar yankawa (daga cikinsu), da kuma abin da aka yanka a kan gumaka, da kuma neman sanin sa'a da kibau. Wannan fasiƙanci ne. A yau kafirai sun ɗebe tsammani daga (karya) addininku, don haka kar ku ji tsoron su, ku ji tsoro Na Ni kaɗai. A yau Na cika muku addininku, kuma Na cika muku ni'imata, kuma Na yardar muku Musulunci ya zamo shi ne addininku. Duk wanda ya matsu (ya ci abin da aka ambata a baya) saboda yunwa, ba yana mai karkata zuwa ga zunubi ba, to lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(4) Suna tambayar ka, mene ne aka halatta musu? Ka ce: "An halatta muku kyawawan abubuwa da kuma abin da dabbobinku da kuka koyar da su (farauta) suka kamo muku, kuna koya musu abin da Allah Ya koya muku, don haka ku ci daga duk abin da suka kamo muku, sannan ku ambaci sunan Allah a kansa; kuma ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Mai gaggawar hisabi ne

(5) A yau an halatta muku kyawawan abubuwa; kuma abincin waɗanda aka bai wa Littafi halal ne a gare ku, ku ma abincinku halal ne a gare su; sannan kuma (Na halatta muku auren) mata kamammu daga cikin muminai, da kuma kamammu daga cikin waɗanda aka bai wa Littafi a gabaninku, idan har kun ba su sadakinsu, kuna masu kame kawunanku, ba kuna mazinata ba, ba kuma kuna masu yin daduro ba. Duk kuwa wanda ya kafirce wa imani, haƙiƙa aikinsa ya rushe, kuma a ranar lahira yana cikin asararru

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا قُمۡتُمۡ إِلَى ٱلصَّلَوٰةِ فَٱغۡسِلُواْ
وُجُوهَكُمۡ وَأَيۡدِيَكُمۡ إِلَى ٱلۡمَرَافِقِ وَٱمۡسَحُواْ بِرُءُوسِكُمۡ
وَأَرۡجُلَكُمۡ إِلَى ٱلۡكَعۡبَيۡنِۚ وَإِن كُنتُمۡ جُنُبٗا فَٱطَّهَّرُواْۚ
وَإِن كُنتُم مَّرۡضَىٰٓ أَوۡ عَلَىٰ سَفَرٍ أَوۡ جَآءَ أَحَدٞ مِّنكُم مِّنَ
ٱلۡغَآئِطِ أَوۡ لَٰمَسۡتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَلَمۡ تَجِدُواْ مَآءٗ فَتَيَمَّمُواْ صَعِيدٗا
طَيِّبٗا فَٱمۡسَحُواْ بِوُجُوهِكُمۡ وَأَيۡدِيكُم مِّنۡهُۚ مَا يُرِيدُ ٱللَّهُ
لِيَجۡعَلَ عَلَيۡكُم مِّنۡ حَرَجٖ وَلَٰكِن يُرِيدُ لِيُطَهِّرَكُمۡ
وَلِيُتِمَّ نِعۡمَتَهُۥ عَلَيۡكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ٦
وَٱذۡكُرُواْ نِعۡمَةَ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ وَمِيثَٰقَهُ ٱلَّذِي وَاثَقَكُم
بِهِۦٓ إِذۡ قُلۡتُمۡ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَاۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمُۢ
بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٧ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُونُواْ قَوَّٰمِينَ
لِلَّهِ شُهَدَآءَ بِٱلۡقِسۡطِۖ وَلَا يَجۡرِمَنَّكُمۡ شَنَـَٔانُ قَوۡمٍ عَلَىٰٓ
أَلَّا تَعۡدِلُواْۚ ٱعۡدِلُواْ هُوَ أَقۡرَبُ لِلتَّقۡوَىٰۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ
ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ٨ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٌ عَظِيمٞ ٩

(6) ku yi salla, to ku wanke fuskokinku da hannayenku zuwa gwiwoyinsu, kuma ku shafi kawunanku, kuma (ku wanke) ƙafafunku zuwa idon sawu. Kuma idan kun kasance masu janaba, to sai ku tsarkaka. Idan kuma kun kasance marasa lafiya, ko a halin tafiya, ko ɗaya daga cikinku ya dawo daga bayan gari, ko kuka sadu da mata, kuma sai ba ku sami ruwa ba, to ku yi taimama a doron ƙasa mai tsarki, ku shafi fuskokinku da hannayenku daga shi. Allah ba Yana nufin Ya sanya ƙunci a tare da ku ba ne, a'a, Yana nufi ne Ya tsarkake ku, kuma Ya cika ni'imarsa a gare ku, don ku zamo masu godiya

(7) Kuma ku tuna ni'imar Allah da Ya yi muku, da alƙawarinsa wanda Ya ƙulla shi da ku, yayin da kuka ce: "Mun ji, kuma za mu yi biyayya!" Kuma ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Masanin abin da ƙiraza suka ƙunsa ne

(8) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku zamo masu tsayawa ƙyam da haƙƙoƙin Allah, kuna masu yin shaida da adalci; kuma kada ƙin waɗansu mutane ya hana ku yi musu adalci. Ku yi adalci shi ne mafi kusanci ga taƙawa. Kuma ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne

(9) Allah Ya yi alƙawari ga waɗanda suka yi imani, kuma suka yi aiki nagari, suna da gafara da kuma lada mai girma

وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَحِيمِ ١٠ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَتَ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ إِذۡ هَمَّ قَوۡمٌ أَن يَبۡسُطُوٓاْ إِلَيۡكُمۡ أَيۡدِيَهُمۡ فَكَفَّ أَيۡدِيَهُمۡ عَنكُمۡۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ١١ ۞ وَلَقَدۡ أَخَذَ ٱللَّهُ مِيثَٰقَ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ وَبَعَثۡنَا مِنۡهُمُ ٱثۡنَيۡ عَشَرَ نَقِيبٗاۖ وَقَالَ ٱللَّهُ إِنِّي مَعَكُمۡۖ لَئِنۡ أَقَمۡتُمُ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَيۡتُمُ ٱلزَّكَوٰةَ وَءَامَنتُم بِرُسُلِي وَعَزَّرۡتُمُوهُمۡ وَأَقۡرَضۡتُمُ ٱللَّهَ قَرۡضًا حَسَنٗا لَّأُكَفِّرَنَّ عَنكُمۡ سَيِّـَٔاتِكُمۡ وَلَأُدۡخِلَنَّكُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۚ فَمَن كَفَرَ بَعۡدَ ذَٰلِكَ مِنكُمۡ فَقَدۡ ضَلَّ سَوَآءَ ٱلسَّبِيلِ ١٢ فَبِمَا نَقۡضِهِم مِّيثَٰقَهُمۡ لَعَنَّٰهُمۡ وَجَعَلۡنَا قُلُوبَهُمۡ قَٰسِيَةٗۖ يُحَرِّفُونَ ٱلۡكَلِمَ عَن مَّوَاضِعِهِۦ وَنَسُواْ حَظّٗا مِّمَّا ذُكِّرُواْ بِهِۦۚ وَلَا تَزَالُ تَطَّلِعُ عَلَىٰ خَآئِنَةٖ مِّنۡهُمۡ إِلَّا قَلِيلٗا مِّنۡهُمۡۖ فَٱعۡفُ عَنۡهُمۡ وَٱصۡفَحۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٣

(10) Kuma waɗanda suka kafirta, suka kuma ƙaryata ayoyinmu, waɗannan su ne ‘yan wuta

(11) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku tuna ni’imar Allah da Ya yi muku, yayin da waɗansu mutane suka yi niyyar shimfiɗa hannayensu a kanku, sai Ya kame muku hannayensu, kuma ku kiyaye dokokin Allah. To sai muminai su dogara ga Allah Shi kaɗai

(12) Kuma lalle haƙiƙa Allah Ya ɗauki alƙawari (daga) Banu-Isra’ila, kuma Mun aiko musu wakilai goma sha biyu daga cikinsu; kuma Allah Ya ce: “Lalle Ni Ina tare da ku; tabbas idan har kuka tsayar da salla, kuma kuka bayar da zakka, kuma kuka yi imani da manzannina, kuma kuka ƙarfafe su, kuma kuka bai wa Allah kyakkyawan rance, to lalle zan kankare muku kurakuranku, kuma zan shigar da ku gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. To duk wanda ya kafirce daga cikinku bayan haka, to haƙiƙa ya ɓace wa tafarki madaidaici.”

(13) Saboda yadda suke warware alƙawarin da aka yi da su, sai Muka la’ance su, kuma Muka sanya zukatansu suka zamo ƙeƙasassu; suna jirkita magana daga wurinta, kuma sun bar wani rabo na abin da aka yi musu wa’azi da shi. Kuma ba za ka gushe ba kana ganin ha’inci daga gare su, sai ‘yan kaɗan daga cikinsu. To sai ka yi musu afuwa, kuma ka kawar da kai, lalle Allah Yana son masu kyautatawa

وَمِنَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّا نَصَٰرَىٰٓ أَخَذۡنَا مِيثَٰقَهُمۡ فَنَسُواْ
حَظّٗا مِّمَّا ذُكِّرُواْ بِهِۦ فَأَغۡرَيۡنَا بَيۡنَهُمُ ٱلۡعَدَٰوَةَ
وَٱلۡبَغۡضَآءَ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ وَسَوۡفَ يُنَبِّئُهُمُ ٱللَّهُ
بِمَا كَانُواْ يَصۡنَعُونَ ١٤ يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ قَدۡ
جَآءَكُمۡ رَسُولُنَا يُبَيِّنُ لَكُمۡ كَثِيرٗا مِّمَّا
كُنتُمۡ تُخۡفُونَ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَيَعۡفُواْ عَن كَثِيرٖۚ
قَدۡ جَآءَكُم مِّنَ ٱللَّهِ نُورٞ وَكِتَٰبٞ مُّبِينٞ ١٥
يَهۡدِي بِهِ ٱللَّهُ مَنِ ٱتَّبَعَ رِضۡوَٰنَهُۥ سُبُلَ ٱلسَّلَٰمِ
وَيُخۡرِجُهُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ بِإِذۡنِهِۦ
وَيَهۡدِيهِمۡ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ١٦ لَّقَدۡ كَفَرَ
ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡمَسِيحُ ٱبۡنُ مَرۡيَمَۚ
قُلۡ فَمَن يَمۡلِكُ مِنَ ٱللَّهِ شَيۡـًٔا إِنۡ أَرَادَ أَن يُهۡلِكَ
ٱلۡمَسِيحَ ٱبۡنَ مَرۡيَمَ وَأُمَّهُۥ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ
جَمِيعٗاۗ وَلِلَّهِ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَاۚ
يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ١٧

(14) Kuma daga cikin waɗanda suka ce: "Lalle mu Nasara ne," su ma Mun riƙi alƙawarinsu, sai suka bar wani kaso na abin da aka yi musu wa'azi da shi, sai Muka iza wutar gaba da ƙiyayya a tsakaninsu har zuwa ranar tashin alƙiyama. Kuma da sannu Allah zai ba su labarin abin da suka kasance suna aikatawa

(15) Ya ku waɗanda aka bai wa Littafi, haƙiƙa Manzonmu ya zo muku, yana bayyana muku da yawa daga cikin abin da kuke ɓoyewa daga Littafin, yana kuma yin afuwa ga abubuwa da dama daga ciki.

Haƙiƙa haske ya zo muku daga Allah, da kuma Littafi mai bayyanawa

(16) Da shi ne Allah Yake shiryar da wanda ya bi yardarsa hanyoyi na aminci, kuma Yake fitar da su daga duffai zuwa ga haske da izininsa, kuma Yana shiryar da su zuwa ga tafarki madaidaici

(17) Lalle haƙiƙa, waɗannan da suka ce: "Lalle Allah Shi ne Almasihu ɗan Maryamu" sun kafirta. Ka ce: "To wane ne ya isa ya hana Allah, idan Ya yi nufin Ya hallaka Almasihu ɗan Maryamu da mahaifiyarsa da duk wanda yake ban ƙasa gaba ɗaya? Allah kuwa Shi Yake mallakar abin da yake cikin sammai da ƙasa da kuma abin da yake tsakaninsu. Yana halittar abin da Ya ga dama. Kuma Allah Mai cikakken iko ne a kan komai."

وَقَالَتِ ٱلْيَهُودُ وَٱلنَّصَٰرَىٰ نَحْنُ أَبْنَٰٓؤُا۟ ٱللَّهِ وَأَحِبَّٰٓؤُهُۥ ۚ قُلْ
فَلِمَ يُعَذِّبُكُم بِذُنُوبِكُم ۖ بَلْ أَنتُم بَشَرٌ مِّمَّنْ خَلَقَ ۚ يَغْفِرُ لِمَن
يَشَآءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ ۚ وَلِلَّهِ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ
وَمَا بَيْنَهُمَا ۖ وَإِلَيْهِ ٱلْمَصِيرُ ﴿١٨﴾ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ قَدْ جَآءَكُمْ
رَسُولُنَا يُبَيِّنُ لَكُمْ عَلَىٰ فَتْرَةٍ مِّنَ ٱلرُّسُلِ أَن تَقُولُوا۟ مَا جَآءَنَا
مِنۢ بَشِيرٍ وَلَا نَذِيرٍ ۖ فَقَدْ جَآءَكُم بَشِيرٌ وَنَذِيرٌ ۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ
شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿١٩﴾ وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦ يَٰقَوْمِ ٱذْكُرُوا۟
نِعْمَةَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ إِذْ جَعَلَ فِيكُمْ أَنۢبِيَآءَ وَجَعَلَكُم مُّلُوكًا
وَءَاتَىٰكُم مَّا لَمْ يُؤْتِ أَحَدًا مِّنَ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٢٠﴾ يَٰقَوْمِ ٱدْخُلُوا۟
ٱلْأَرْضَ ٱلْمُقَدَّسَةَ ٱلَّتِى كَتَبَ ٱللَّهُ لَكُمْ وَلَا تَرْتَدُّوا۟
عَلَىٰٓ أَدْبَٰرِكُمْ فَتَنقَلِبُوا۟ خَٰسِرِينَ ﴿٢١﴾ قَالُوا۟ يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّ
فِيهَا قَوْمًا جَبَّارِينَ وَإِنَّا لَن نَّدْخُلَهَا حَتَّىٰ يَخْرُجُوا۟ مِنْهَا فَإِن
يَخْرُجُوا۟ مِنْهَا فَإِنَّا دَٰخِلُونَ ﴿٢٢﴾ قَالَ رَجُلَانِ مِنَ ٱلَّذِينَ يَخَافُونَ
أَنْعَمَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمَا ٱدْخُلُوا۟ عَلَيْهِمُ ٱلْبَابَ فَإِذَا دَخَلْتُمُوهُ فَإِنَّكُمْ
غَٰلِبُونَ ۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَتَوَكَّلُوٓا۟ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٢٣﴾

(18) Kuma Yahudawa da Nasara suka ce: "Mu 'ya'yan Allah ne, kuma masoyansa." Ka ce: "To don me Yake muku azaba a sanadiyyar zunubanku? Ba haka ne ba, ku mutane ne daga cikin waɗanda Ya halitta. Yana yin gafara ga wanda Ya ga dama, kuma Yana yin azaba ga wanda Ya ga dama. Kuma mulkin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu na Allah ne, kuma zuwa gare Shi ne makoma take."

(19) Ya ku waɗanda aka bai wa Littafi, haƙiƙa Manzonmu ya zo muku, yana yi muku bayani bayan yankewar manzanci, don kar ku ce: "Ba wani mai bushara da ya zo mana, ko wani mai gargaɗi." To haƙiƙa mai busharar, kuma mai gargaɗin, ya zo muku. Kuma Allah Mai iko ne a kan komai

(20) Kuma (ka tuna) lokacin da Musa ya ce wa mutanensa: "Ya ku mutanena, ku tuna ni'imar Allah da Ya yi muku, yayin da Ya sanya annabawa da yawa a cikinku, kuma Ya sanya ku sarakuna, kuma Ya ba ku irin abin da bai ba wa wani cikin talikai ba

(21) "Ya ku mutanena, ku shiga ƙasar nan mai tsarki[1], wadda Allah Ya wajabta muku (shigarta), kuma kada ku yarda ku juya baya, sai ku komo kuna hasararru."

(22) Suka ce, "Ya kai Musa, lalle a cikinta akwai waɗansu mutane masu tsananin ƙarfi, kuma mu ba za mu shige ta ba har sai sun fita daga cikinta, don haka idan suka fita daga cikinta, to lalle za mu shiga."

(23) Waɗansu mutane biyu daga cikin masu jin tsoron (Allah), waɗanda Allah Ya yi musu ni'ima (ta imani), suka ce: "Ku shigar musu ta ƙofar (garin); idan har kun shige shi, to lalle ku masu cin nasara ne. Kuma ga Allah kaɗai za ku dogara, idan kun kasance ku muminai ne."

(1) Kasa mai tsarki ita ce Baitul Maƙdis.

قَالُوا۟ يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّا لَن نَّدْخُلَهَآ أَبَدًا مَّا دَامُوا۟ فِيهَا فَٱذْهَبْ
أَنتَ وَرَبُّكَ فَقَٰتِلَآ إِنَّا هَٰهُنَا قَٰعِدُونَ ﴿٢٤﴾ قَالَ رَبِّ إِنِّى
لَآ أَمْلِكُ إِلَّا نَفْسِى وَأَخِى ۖ فَٱفْرُقْ بَيْنَنَا وَبَيْنَ ٱلْقَوْمِ
ٱلْفَٰسِقِينَ ﴿٢٥﴾ قَالَ فَإِنَّهَا مُحَرَّمَةٌ عَلَيْهِمْ أَرْبَعِينَ سَنَةً ۛ
يَتِيهُونَ فِى ٱلْأَرْضِ ۗ فَلَا تَأْسَ عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْفَٰسِقِينَ
﴿٢٦﴾ ۞ وَٱتْلُ عَلَيْهِمْ نَبَأَ ٱبْنَىْ ءَادَمَ بِٱلْحَقِّ ۘ إِذْ قَرَّبَا قُرْبَانًا فَتُقُبِّلَ
مِنْ أَحَدِهِمَا وَلَمْ يُتَقَبَّلْ مِنَ ٱلْءَاخَرِ ۚ قَالَ لَأَقْتُلَنَّكَ ۖ
قَالَ إِنَّمَا يَتَقَبَّلُ ٱللَّهُ مِنَ ٱلْمُتَّقِينَ ﴿٢٧﴾ لَئِنۢ بَسَطتَ إِلَىَّ يَدَكَ
لِتَقْتُلَنِى مَآ أَنَا۠ بِبَاسِطٍ يَدِىَ إِلَيْكَ لِأَقْتُلَكَ ۖ إِنِّىٓ أَخَافُ ٱللَّهَ
رَبَّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٢٨﴾ إِنِّىٓ أُرِيدُ أَن تَبُوٓأَ بِإِثْمِى وَإِثْمِكَ فَتَكُونَ
مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلنَّارِ ۚ وَذَٰلِكَ جَزَٰٓؤُا۟ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٢٩﴾ فَطَوَّعَتْ
لَهُۥ نَفْسُهُۥ قَتْلَ أَخِيهِ فَقَتَلَهُۥ فَأَصْبَحَ مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿٣٠﴾
فَبَعَثَ ٱللَّهُ غُرَابًا يَبْحَثُ فِى ٱلْأَرْضِ لِيُرِيَهُۥ كَيْفَ يُوَٰرِى
سَوْءَةَ أَخِيهِ ۚ قَالَ يَٰوَيْلَتَىٰٓ أَعَجَزْتُ أَنْ أَكُونَ مِثْلَ هَٰذَا
ٱلْغُرَابِ فَأُوَٰرِىَ سَوْءَةَ أَخِى ۖ فَأَصْبَحَ مِنَ ٱلنَّٰدِمِينَ ﴿٣١﴾

(24) Suka ce; "Ya kai Musa, lalle mu fa ba za mu taɓa shigar ta ba har abada, matuƙar suna cikinta; sai ka je kai da Ubangijinka ku yi yaƙin, lalle mu kam muna nan a zaune."

(25) Ya ce: "Ya Ubangijina, lalle ni ban mallaki kowa ba sai kaina da ɗan'uwana; don haka Ka yi hukunci tsakaninmu da mutanen da suke fasiƙai."

(26) Ya ce: "To lalle an haramta musu (shigarta) har tsawon shekara arba'in. Za su yi ta ɗimuwa a bayan ƙasa. Don haka kada ka yi baƙin ciki a kan mutanen da suke fasiƙai."

(27) Kuma ka karanta musu labarin gaskiya na 'ya'yan Adamu su biyu, yayin da suka gabatar da wani abin neman lada, sai aka karɓi na ɗaya daga cikinsu, ɗayan kuma ba a karɓi nasa ba, sai ya ce: "Wallahi, sai na kashe ka!" Sai ya ce: "Allah Yana karɓar aiki ne kawai daga masu taƙawa

(28) "Wallahi, idan har ka miƙa hannunka gare ni domin ka kashe ni, ni kam ba zan miƙa hannuna gare ka don in kashe ka ba; lalle ni ina jin tsoron Allah Ubangijin talikai

(29) "Lalle ni ina son ka ɗauki zunubina da zunubinka, sai ka kasance daga cikin 'yan wuta. Kuma wannan shi ne sakamakon azzalumai."

(30) Sai zuciyarsa ta ƙawata masa ya kashe ɗan'uwansa, sai ya kashe shi, sai ya zama cikin hasararru[1]

(31) Sai Allah Ya aiko da wani hankaka ya riƙa tona ƙasa don ya nuna masa yadda zai binne gawar ɗan'uwansa. Sai ya ce: "Kaicona! Yanzu na kasa zama kamar wannan hankakan, in je in binne gawar ɗan'uwana?" Sai ya wayi gari cikin masu nadama

(1) Wannan shi ne ɗan'adam na farko da ya fara kisan kai a duniya, don haka yana da kamasho a cikin kowane jini da za a zubar har zuwa tashin alƙiyam..

مِنْ أَجْلِ ذَٰلِكَ كَتَبْنَا عَلَىٰ بَنِيٓ إِسْرَٰٓءِيلَ أَنَّهُۥ مَن قَتَلَ
نَفْسًۢا بِغَيْرِ نَفْسٍ أَوْ فَسَادٍ فِى ٱلْأَرْضِ فَكَأَنَّمَا قَتَلَ
ٱلنَّاسَ جَمِيعًا وَمَنْ أَحْيَاهَا فَكَأَنَّمَآ أَحْيَا ٱلنَّاسَ
جَمِيعًا ۚ وَلَقَدْ جَآءَتْهُمْ رُسُلُنَا بِٱلْبَيِّنَٰتِ ثُمَّ إِنَّ كَثِيرًا
مِّنْهُم بَعْدَ ذَٰلِكَ فِى ٱلْأَرْضِ لَمُسْرِفُونَ ﴿٣٢﴾ إِنَّمَا
جَزَٰٓؤُا۟ ٱلَّذِينَ يُحَارِبُونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَسْعَوْنَ فِى
ٱلْأَرْضِ فَسَادًا أَن يُقَتَّلُوٓا۟ أَوْ يُصَلَّبُوٓا۟ أَوْ تُقَطَّعَ أَيْدِيهِمْ
وَأَرْجُلُهُم مِّنْ خِلَٰفٍ أَوْ يُنفَوْا۟ مِنَ ٱلْأَرْضِ ۚ ذَٰلِكَ
لَهُمْ خِزْىٌ فِى ٱلدُّنْيَا ۖ وَلَهُمْ فِى ٱلْءَاخِرَةِ عَذَابٌ عَظِيمٌ
﴿٣٣﴾ إِلَّا ٱلَّذِينَ تَابُوا۟ مِن قَبْلِ أَن تَقْدِرُوا۟ عَلَيْهِمْ ۖ فَٱعْلَمُوٓا۟
أَنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٣٤﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱتَّقُوا۟
ٱللَّهَ وَٱبْتَغُوٓا۟ إِلَيْهِ ٱلْوَسِيلَةَ وَجَٰهِدُوا۟ فِى سَبِيلِهِۦ
لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿٣٥﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لَوْ أَنَّ لَهُم
مَّا فِى ٱلْأَرْضِ جَمِيعًا وَمِثْلَهُۥ مَعَهُۥ لِيَفْتَدُوا۟ بِهِۦ مِنْ
عَذَابِ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ مَا تُقُبِّلَ مِنْهُمْ ۖ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٣٦﴾

(32) Saboda wannan ne muka wajabta wa Banu-Isra'ila cewa, duk wanda ya kashe wani rai ba tare da (laifin kisan) kai ba, ko kuma wata ɓarna a bayan ƙasa, to kamar ya kashe mutane ne gaba ɗaya, wanda kuwa ya raya shi, to kamar ya raya mutane ne gaba ɗaya. Kuma lalle hakika manzanninmu sun zo musu da (hujjoji) mabayyana, amma sai ga shi da yawa daga cikinsu bayan hakan, lalle masu ɓarna ne a bayan ƙasa

(33) Lalle sakamakon waɗanda suke yaƙar Allah da Manzonsa, kuma suke ɓarna a bayan ƙasa[1], shi ne kawai a karkashe su ko kuma a giggicciye su ko kuma a yayyanke hannayensu da ƙafafuwansu a tarnaƙe ko kuma a kore su daga ƙasa. Wannan ƙasƙanci ne a gare su a nan duniya, a lahira kuma suna da azaba mai girma

(34) Sai dai waɗanda suka tuba tun kafin ku sami damar kama su; to ku sani cewa, lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(35) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku nemi abin da zai sada ku da shi, kuma ku yi jihadi wajen yaɗa kalmarsa, don ku rabauta

(36) Lalle waɗanda suka kafirta, in da a ce duk abin da yake ban ƙasa gaba ɗaya nasu ne, haɗe kuma da wani kamarsa, domin su fanshi kansu da shi daga azabar ranar tashin alƙiyama, da ba za a karɓa daga gare su ba; kuma suna da azaba mai raɗaɗi

(1) Ana nufin duk wasu masu ta'addanci da aikata fashi da makami, wannan shi ne hukuncinsu.

يُرِيدُونَ أَن يَخْرُجُوا۟ مِنَ ٱلنَّارِ وَمَا هُم بِخَٰرِجِينَ مِنْهَا ۖ
وَلَهُمْ عَذَابٌ مُّقِيمٌ ﴿٣٧﴾ وَٱلسَّارِقُ وَٱلسَّارِقَةُ فَٱقْطَعُوٓا۟
أَيْدِيَهُمَا جَزَآءًۢ بِمَا كَسَبَا نَكَٰلًا مِّنَ ٱللَّهِ ۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ
حَكِيمٌ ﴿٣٨﴾ فَمَن تَابَ مِنۢ بَعْدِ ظُلْمِهِۦ وَأَصْلَحَ فَإِنَّ ٱللَّهَ
يَتُوبُ عَلَيْهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٣٩﴾ أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ
لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ يُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ وَيَغْفِرُ
لِمَن يَشَآءُ ۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٤٠﴾ ۞ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلرَّسُولُ لَا يَحْزُنكَ ٱلَّذِينَ يُسَٰرِعُونَ فِى ٱلْكُفْرِ مِنَ
ٱلَّذِينَ قَالُوٓا۟ ءَامَنَّا بِأَفْوَٰهِهِمْ وَلَمْ تُؤْمِن قُلُوبُهُمْ ۛ وَمِنَ
ٱلَّذِينَ هَادُوا۟ ۛ سَمَّٰعُونَ لِلْكَذِبِ سَمَّٰعُونَ لِقَوْمٍ
ءَاخَرِينَ لَمْ يَأْتُوكَ ۖ يُحَرِّفُونَ ٱلْكَلِمَ مِنۢ بَعْدِ مَوَاضِعِهِۦ ۖ
يَقُولُونَ إِنْ أُوتِيتُمْ هَٰذَا فَخُذُوهُ وَإِن لَّمْ تُؤْتَوْهُ
فَٱحْذَرُوا۟ ۚ وَمَن يُرِدِ ٱللَّهُ فِتْنَتَهُۥ فَلَن تَمْلِكَ لَهُۥ مِنَ ٱللَّهِ
شَيْـًٔا ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَمْ يُرِدِ ٱللَّهُ أَن يُطَهِّرَ قُلُوبَهُمْ ۚ لَهُمْ
فِى ٱلدُّنْيَا خِزْىٌ ۖ وَلَهُمْ فِى ٱلْءَاخِرَةِ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿٤١﴾

(37) Suna nufin su fita daga cikin wuta, alhalin su ba masu fita ne daga cikinta ba; kuma suna da wata azaba madawwamiya
(38) Kuma ɓarawo da ɓarauniya, sai ku yanke hannayensu[1], wannan sakamako ne na abin da suka aikata, uƙuba ce daga Allah. Kuma Allah Mabuwayi ne, Mai hikima
(39) To (amma) wanda ya tuba bayan zaluncinsa, kuma ya gyara aikinsa, to lalle Allah zai karɓi tubansa. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai
(40) Shin ba ka da masaniyar cewa, lalle Allah Shi ne Yake mallakar abin da yake cikin sammai da kuma ƙasa, Yana yin azaba ga wanda Ya ga dama, kuma Yana gafarta wa wanda Ya ga dama. Kuma Allah Mai iko ne a kan komai?
(41) Ya kai wannan Manzo, kar waɗannan da suke gaggawa cikin kafirci su baƙanta maka rai, daga cikin waɗanda suka ce: "Mun yi imani" da bakunansu, amma zukatansu ba su yi imani ba; da kuma waɗanda suke Yahudawa, masu yawan sauraron ƙarya, masu yawan sauraron waɗansu mutanen da ba su zo wajenka ba[2]; suna caccanja kalmomi daga wurarensu, suna cewa: "Idan an ba ku wannan, to ku karɓe shi, idan kuwa ba shi aka ba ku ba, to ku yi hattara[3]." Duk kuwa wanda Allah Ya nufi fitinar sa, to ba abin da za ka iya mallaka masa daga wurin Allah. Waɗannan su ne waɗanda Allah bai yi nufin Ya tsarkake zukatansu ba. a nan duniya suna da ƙasƙanci, a lahira kuma suna da azaba mai girma

(1) Za a yanke hannayensu ne na dama daga tsintsiyar hannu. Sunna ta bayyana cewa ana yanke hannun ɓarawon da ya yi satar kai rubu'in dinare ko dirhami uku na azurfa ko abin da ya yi daidai da su.

(2) Su ne malamansu da shugabanninsu waɗanda ba sa halartar majalisin Manzon Allah ( ).

(3) Watau suna faɗa wa mabiyansu cewa, su kai ƙara wurin Manzon Allah ( ), idan ya yi musu hukuncin da ya dace da son zuciyarsu su karɓa, idan kuwa ya yi musu hukuncin da ya saɓa wa son zuciyarsu, to kada su yarda.

سَمَّٰعُونَ لِلْكَذِبِ أَكَّٰلُونَ لِلسُّحْتِ ۚ فَإِن جَآءُوكَ
فَٱحْكُم بَيْنَهُمْ أَوْ أَعْرِضْ عَنْهُمْ ۖ وَإِن تُعْرِضْ عَنْهُمْ فَلَن
يَضُرُّوكَ شَيْـًٔا ۖ وَإِنْ حَكَمْتَ فَٱحْكُم بَيْنَهُم بِٱلْقِسْطِ ۚ
إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُقْسِطِينَ ﴿٤٢﴾ وَكَيْفَ يُحَكِّمُونَكَ
وَعِندَهُمُ ٱلتَّوْرَىٰةُ فِيهَا حُكْمُ ٱللَّهِ ثُمَّ يَتَوَلَّوْنَ مِنۢ بَعْدِ
ذَٰلِكَ ۚ وَمَآ أُو۟لَٰٓئِكَ بِٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٤٣﴾ إِنَّآ أَنزَلْنَا ٱلتَّوْرَىٰةَ
فِيهَا هُدًى وَنُورٌ ۚ يَحْكُمُ بِهَا ٱلنَّبِيُّونَ ٱلَّذِينَ أَسْلَمُوا۟
لِلَّذِينَ هَادُوا۟ وَٱلرَّبَّٰنِيُّونَ وَٱلْأَحْبَارُ بِمَا ٱسْتُحْفِظُوا۟ مِن
كِتَٰبِ ٱللَّهِ وَكَانُوا۟ عَلَيْهِ شُهَدَآءَ ۚ فَلَا تَخْشَوُا۟ ٱلنَّاسَ
وَٱخْشَوْنِ وَلَا تَشْتَرُوا۟ بِـَٔايَٰتِى ثَمَنًا قَلِيلًا ۚ وَمَن لَّمْ يَحْكُم
بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿٤٤﴾ وَكَتَبْنَا
عَلَيْهِمْ فِيهَآ أَنَّ ٱلنَّفْسَ بِٱلنَّفْسِ وَٱلْعَيْنَ بِٱلْعَيْنِ وَٱلْأَنفَ
بِٱلْأَنفِ وَٱلْأُذُنَ بِٱلْأُذُنِ وَٱلسِّنَّ بِٱلسِّنِّ وَٱلْجُرُوحَ
قِصَاصٌ ۚ فَمَن تَصَدَّقَ بِهِۦ فَهُوَ كَفَّارَةٌ لَّهُۥ ۚ وَمَن
لَّمْ يَحْكُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٤٥﴾

(42) (Su ne) masu yawan sauraron ƙarya, masu yawan cin haram. Don haka idan sun zo maka, to ka yi musu hukunci, ko ka kau da kai daga gare su; idan kuwa ka kawar da kai daga gare su, to ba za su cutar da kai da komai ba; idan kuwa za ka yi hukuncin, to ka yi hukunci tsakaninsu da adalci. Lalle Allah Yana son masu adalci
(43) Kuma ta yaya za su kawo maka hukunci, alhalin Attaura tana wurinsu, a cikinta akwai hukuncin Allah, sannan su juya baya bayan haka? Waɗannan kam ba muminai ba ne
(44) Lalle Mu Muka saukar da Attaura, (wadda) a cikinta akwai shiriya da haske. Annabawa waɗanda suka miƙa wuya suna hukunci da ita, ga waɗanda suke Yahudawa, da malamai na-Allah da malamai masana, saboda abin da aka ɗora musu na kiyaye Littafin Allah, kuma sun kasance masu ba da shaida a kansa. Don haka kada ku ji tsoron mutane, ku ji tsoro Na Ni kaɗai, kuma kada ku musanya ayoyina da wani ɗan farashi ƙanƙani. Duk wanda bai yi hukunci da abin da Allah Ya saukar ba kuwa, to waɗannan su ne kafirai
(45) Kuma Mun wajabta a kansu a cikinta (Attaura), lalle rai da rai, kuma ido da ido, kuma hanci da hanci, kuma kunne da kunne, kuma haƙori da haƙori, raunuka kuma a yi ramuwa. To duk wanda ya yi sadaka da shi, to wannan kaffara ce gare shi. Duk wanda bai yi hukunci da abin da Allah Ya saukar ba kuwa, to waɗannan su ne azzalumai

وَقَفَّيْنَا عَلَىٰٓ ءَاثَـٰرِهِم بِعِيسَى ٱبْنِ مَرْيَمَ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ
مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ ۖ وَءَاتَيْنَـٰهُ ٱلْإِنجِيلَ فِيهِ هُدًى وَنُورٌ وَمُصَدِّقًا
لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ وَهُدًى وَمَوْعِظَةً لِّلْمُتَّقِينَ ﴿٤٦﴾
وَلْيَحْكُمْ أَهْلُ ٱلْإِنجِيلِ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فِيهِ ۚ وَمَن لَّمْ يَحْكُم
بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فَأُو۟لَـٰٓئِكَ هُمُ ٱلْفَـٰسِقُونَ ﴿٤٧﴾ وَأَنزَلْنَآ إِلَيْكَ
ٱلْكِتَـٰبَ بِٱلْحَقِّ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ مِنَ ٱلْكِتَـٰبِ
وَمُهَيْمِنًا عَلَيْهِ ۖ فَٱحْكُم بَيْنَهُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ ۖ وَلَا تَتَّبِعْ أَهْوَآءَهُمْ
عَمَّا جَآءَكَ مِنَ ٱلْحَقِّ ۚ لِكُلٍّ جَعَلْنَا مِنكُمْ شِرْعَةً وَمِنْهَاجًا ۚ
وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَكُمْ أُمَّةً وَٰحِدَةً وَلَـٰكِن لِّيَبْلُوَكُمْ
فِى مَآ ءَاتَىٰكُمْ ۖ فَٱسْتَبِقُوا۟ ٱلْخَيْرَٰتِ ۚ إِلَى ٱللَّهِ مَرْجِعُكُمْ جَمِيعًا
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ فِيهِ تَخْتَلِفُونَ ﴿٤٨﴾ وَأَنِ ٱحْكُم بَيْنَهُم
بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ وَلَا تَتَّبِعْ أَهْوَآءَهُمْ وَٱحْذَرْهُمْ أَن يَفْتِنُوكَ عَنۢ
بَعْضِ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ إِلَيْكَ ۖ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَٱعْلَمْ أَنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ أَن يُصِيبَهُم
بِبَعْضِ ذُنُوبِهِمْ ۗ وَإِنَّ كَثِيرًا مِّنَ ٱلنَّاسِ لَفَـٰسِقُونَ ﴿٤٩﴾ أَفَحُكْمَ
ٱلْجَـٰهِلِيَّةِ يَبْغُونَ ۚ وَمَنْ أَحْسَنُ مِنَ ٱللَّهِ حُكْمًا لِّقَوْمٍ يُوقِنُونَ ﴿٥٠﴾

(46) Sai Muka biyar da Isa ɗan Maryamu a bayansu wanda yake gaskata abin da ya gabace shi na Attaura, kuma Muka ba shi Linjila, a cikinta akwai shiriya da haske, kuma tana gaskata abin da ya gabace ta na Attaura, kuma shiriya ce, da wa'azi ga masu taƙawa

(47) Lalle kuma ma'abota Linjila su yi hukunci da abin da Allah Ya saukar a cikinsa. Duk wanda bai yi hukunci da abin da Allah Ya saukar ba kuwa, to waɗannan su ne fasiƙai

(48) Kuma Mun saukar maka da Littafin (Alƙur'ani) da gaskiya, yana mai gaskata abin da ya gabace shi na sauran littattafai, kuma mai ɗaukaka a kansu; don haka ka yi hukunci a tsakaninsu da abin da Allah Ya saukar; kuma kada ka bi soye-soyen zukatansu ka bar abin da ya zo maka na gaskiya don bin son zuciyarsu. Kowanne daga cikinku Mun sanya musu tsari na shari'a da tsari na rayuwa. Kuma in da Allah Ya ga dama, da sai Ya sanya ku ku zamo al'umma ɗaya, sai dai kuma don Ya jarrabe ku cikin abin da Ya ba ku; don haka sai ku yi gaggawar aikata ayyuka na alheri. Gaba ɗaya makomarku zuwa ga Allah take, kuma zai ba ku labarin abin da kuka kasance kuna saɓani a kansa

(49) Kuma ka yi hukunci a tsakaninsu da abin da Allah Ya saukar, kuma kada ka bi soye-soyen zukatansu, kuma ka yi hattara da su, don kada su fitine ka ka bar wani sashi na abin da Allah Ya saukar maka; idan kuwa sun juya baya, to ka sani lalle Allah Yana nufin Ya kama su ne da wani sashi na zunubansu. Kuma lalle yawancin mutane fasiƙai ne

(50) Shin hukuncin jahiliyya suke nema ne? To wane ne ya fi Allah kyakkyawan hukunci ga mutanen da suke da sakankancewa?


*يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ ٱلۡيَهُودَ وَٱلنَّصَٰرَىٰٓ أَوۡلِيَآءَۘ بَعۡضُهُمۡ
أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٖۚ وَمَن يَتَوَلَّهُم مِّنكُمۡ فَإِنَّهُۥ مِنۡهُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ
ٱلظَّٰلِمِينَ ٥١ فَتَرَى ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ يُسَٰرِعُونَ فِيهِمۡ يَقُولُونَ
نَخۡشَىٰٓ أَن تُصِيبَنَا دَآئِرَةٞۚ فَعَسَى ٱللَّهُ أَن يَأۡتِيَ بِٱلۡفَتۡحِ أَوۡ أَمۡرٖ مِّنۡ عِندِهِۦ
فَيُصۡبِحُواْ عَلَىٰ مَآ أَسَرُّواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۡ نَٰدِمِينَ ٥٢ وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ
أَهَٰٓؤُلَآءِ ٱلَّذِينَ أَقۡسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهۡدَ أَيۡمَٰنِهِمۡ إِنَّهُمۡ لَمَعَكُمۡۚ حَبِطَتۡ
أَعۡمَٰلُهُمۡ فَأَصۡبَحُواْ خَٰسِرِينَ ٥٣ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَن يَرۡتَدَّ
مِنكُمۡ عَن دِينِهِۦ فَسَوۡفَ يَأۡتِي ٱللَّهُ بِقَوۡمٖ يُحِبُّهُمۡ وَيُحِبُّونَهُۥٓ أَذِلَّةٍ
عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ أَعِزَّةٍ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ يُجَٰهِدُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَا
يَخَافُونَ لَوۡمَةَ لَآئِمٖۚ ذَٰلِكَ فَضۡلُ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ
عَلِيمٌ ٥٤ إِنَّمَا وَلِيُّكُمُ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ
ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُمۡ رَٰكِعُونَ ٥٥ وَمَن يَتَوَلَّ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ
وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فَإِنَّ حِزۡبَ ٱللَّهِ هُمُ ٱلۡغَٰلِبُونَ ٥٦ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
لَا تَتَّخِذُواْ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ دِينَكُمۡ هُزُوٗا وَلَعِبٗا مِّنَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ
ٱلۡكِتَٰبَ مِن قَبۡلِكُمۡ وَٱلۡكُفَّارَ أَوۡلِيَآءَۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٥٧

(51) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku riƙi Yahudawa da Nasara masoya. Sashinsu masoya sashi ne. Duk kuwa cikinku wanda ya jiɓinci lamarinsu, to lalle shi yana cikinsu. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutane azzalumai

(52) Sai ka ga waɗanda suke da cuta a cikin zukatansu suna gaggawa a ciki (jiɓintar su), suna cewa: "Muna jin tsoron kar wata musiba ta same mu." To mai yiwuwa ne Allah Ya zo da buɗi ko wani lamari daga gare Shi, sai su wayi gari suna nadama kan abin da suka rika ɓoyewa a zukatansu

(53) Kuma waɗanda suka yi imani suna cewa[1]: "Yanzu waɗannan su ne waɗanda suka rantse da Allah iya ƙurewar rantsuwarsu; cewa, lalle suna tare da ku?" Ayyukansu sun rushe, don haka sai suka wayi gari suna masu hasara

(54) Ya ku waɗanda suka yi imani, duk wanda ya yi ridda daga cikinku, ya bar addininsa, to (ya sani) Allah zai kawo waɗansu mutane da Yake son su suna son Sa, suna masu ƙasƙantar da kai ga muminai, suna masu nuna wa kafirai isa, suna yin jihadi don ɗaukaka kalmar Allah, kuma ba sa jin tsoron zargin wani mai zargi. Wannan falalar Allah ce da Yake bayar da ita ga wanda Ya ga dama. Kuma Allah Mayalwaci ne, Masani

(55) Allah ne kaɗai Majiɓincin al'amarinku da Manzonsa da kuma waɗanda suka yi imani, waɗanda suke tsayar da salla, kuma suke bayar da zakka, suna kuma masu yin ruku'i

(56) Kuma duk wanda ya jiɓinci Allah da Manzonsa da waɗanda suka yi imani, to lalle rundunar Allah su ne masu rinjaye

(57) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku riƙi waɗanda suke yin izgili da wasa da addininku, waɗanda aka bai wa Littafi tun kafinku, da kuma kafirai, a matsayin masoya, kuma ku kiyaye dokokin Allah, in har da gaske ku muminai ne

(1) Watau lokacin da asirin munafukai ya tonu.

وَإِذَا نَادَيْتُمْ إِلَى ٱلصَّلَوٰةِ ٱتَّخَذُوهَا هُزُوًا وَلَعِبًا ۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَوْمٌ
لَّا يَعْقِلُونَ ﴿٥٨﴾ قُلْ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ هَلْ تَنقِمُونَ مِنَّآ إِلَّآ أَنْ ءَامَنَّا
بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيْنَا وَمَآ أُنزِلَ مِن قَبْلُ وَأَنَّ أَكْثَرَكُمْ فَٰسِقُونَ ﴿٥٩﴾
قُلْ هَلْ أُنَبِّئُكُم بِشَرٍّ مِّن ذَٰلِكَ مَثُوبَةً عِندَ ٱللَّهِ ۚ مَن لَّعَنَهُ ٱللَّهُ وَغَضِبَ
عَلَيْهِ وَجَعَلَ مِنْهُمُ ٱلْقِرَدَةَ وَٱلْخَنَازِيرَ وَعَبَدَ ٱلطَّٰغُوتَ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ شَرٌّ
مَّكَانًا وَأَضَلُّ عَن سَوَآءِ ٱلسَّبِيلِ ﴿٦٠﴾ وَإِذَا جَآءُوكُمْ قَالُوٓا۟ ءَامَنَّا وَقَد
دَّخَلُوا۟ بِٱلْكُفْرِ وَهُمْ قَدْ خَرَجُوا۟ بِهِۦ ۚ وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا كَانُوا۟ يَكْتُمُونَ
﴿٦١﴾ وَتَرَىٰ كَثِيرًا مِّنْهُمْ يُسَٰرِعُونَ فِى ٱلْإِثْمِ وَٱلْعُدْوَٰنِ وَأَكْلِهِمُ
ٱلسُّحْتَ ۚ لَبِئْسَ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٦٢﴾ لَوْلَا يَنْهَىٰهُمُ ٱلرَّبَّٰنِيُّونَ
وَٱلْأَحْبَارُ عَن قَوْلِهِمُ ٱلْإِثْمَ وَأَكْلِهِمُ ٱلسُّحْتَ ۚ لَبِئْسَ مَا كَانُوا۟
يَصْنَعُونَ ﴿٦٣﴾ وَقَالَتِ ٱلْيَهُودُ يَدُ ٱللَّهِ مَغْلُولَةٌ ۚ غُلَّتْ أَيْدِيهِمْ وَلُعِنُوا۟
بِمَا قَالُوا۟ ۘ بَلْ يَدَاهُ مَبْسُوطَتَانِ يُنفِقُ كَيْفَ يَشَآءُ ۚ وَلَيَزِيدَنَّ كَثِيرًا
مِّنْهُم مَّآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ طُغْيَٰنًا وَكُفْرًا ۚ وَأَلْقَيْنَا بَيْنَهُمُ ٱلْعَدَٰوَةَ
وَٱلْبَغْضَآءَ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ ۚ كُلَّمَآ أَوْقَدُوا۟ نَارًا لِّلْحَرْبِ أَطْفَأَهَا
ٱللَّهُ ۚ وَيَسْعَوْنَ فِى ٱلْأَرْضِ فَسَادًا ۚ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿٦٤﴾

(58) Kuma idan kuka yi kiran salla, sai su ɗauke ta abin yi wa izgili da wasa. Suna yin hakan don su mutane ne da ba sa hankalta

(59) Ka ce: "Ya ku Ma'abota Littafi, shin kuna da abin da kuke ƙi a tare da mu ne? Sai fa cewa, mun yi imani da Allah da abin da aka saukar mana da abin da aka saukar kafinmu da kuma cewa, lalle yawancinku fasiƙai ne."

(60) Ka ce: "Shin ba na ba ku labarin sakamakon da ya fi wannan sharri a wurin Allah ba? Shi ne wanda Allah Ya la'anta, kuma Ya yi fushi da shi, kuma Ya mayar da wasu daga cikinsu birrai da aladu; kuma ya bauta wa gunki. Su waɗannan su ne matsayinsu ya fi sharri, kuma (su ne) suka fi ɓacewa daga tafarkin shiriya."

(61) Kuma idan suka zo muku, sai su ce: "Mun yi imani", alhali kuwa haƙiƙa sun shigo da kafirci ne, kuma haƙiƙa sun fita da shi ne. Allah kuwa Shi ne Mafi sanin abin da suka kasance suna ɓoyewa

(62) Kuma za ka ga yawancinsu suna yin gaggawa wajen aikin saɓo da ƙetare iyaka da kuma cin haramun. Lalle tir da abin da suka kasance suna aikatawa

(63)Me ya hana malamansu na Allah da masanansu ba su kwaɓe su daga yin maganar saɓo da cin haram ba? Tir da abin da suka kasance suna aikatawa

(64) Kuma Yahudawa suka ce: "Hannun Allah a ƙuƙunce yake."[1] To an ƙuƙunce hannayensu, kuma an la'ance su sakamakon abin da suka faɗa. Kuma ba haka ba ne. Hannayensa a shimfiɗe suke; Yana ciyarwa yadda Ya ga dama. Kuma abin da aka saukar maka daga wajen Ubangijinka lalle yana daɗa wa yawancinsu shisshigi da kafirci. Kuma Mun jefa gaba da ƙiyayya a tsakankaninsu har zuwa ranar tashin alƙiyama. Duk lokacin da suka yi yunƙurin rura wutar yaƙi, sai Allah Ya bice ta; kuma suna masu tafiya a bayan ƙasa suna aikata ɓarna. Allah kuwa ba Ya son maɓarnata

(1) watau suna nufin ba ya kyauta. Allah ( ) ya tsarkaka daga wannan mummunar magana tasu.

وَلَوْ أَنَّ أَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ ءَامَنُوا۟ وَٱتَّقَوْا۟ لَكَفَّرْنَا عَنْهُمْ
سَيِّـَٔاتِهِمْ وَلَأَدْخَلْنَٰهُمْ جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ﴿٦٥﴾ وَلَوْ أَنَّهُمْ أَقَامُوا۟
ٱلتَّوْرَىٰةَ وَٱلْإِنجِيلَ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيْهِم مِّن رَّبِّهِمْ لَأَكَلُوا۟
مِن فَوْقِهِمْ وَمِن تَحْتِ أَرْجُلِهِم ۚ مِّنْهُمْ أُمَّةٌ مُّقْتَصِدَةٌ ۖ
وَكَثِيرٌ مِّنْهُمْ سَآءَ مَا يَعْمَلُونَ ﴿٦٦﴾ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلرَّسُولُ
بَلِّغْ مَآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ ۖ وَإِن لَّمْ تَفْعَلْ فَمَا بَلَّغْتَ
رِسَالَتَهُۥ ۚ وَٱللَّهُ يَعْصِمُكَ مِنَ ٱلنَّاسِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ
ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٦٧﴾ قُلْ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ لَسْتُمْ عَلَىٰ شَىْءٍ حَتَّىٰ
تُقِيمُوا۟ ٱلتَّوْرَىٰةَ وَٱلْإِنجِيلَ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيْكُم مِّن رَّبِّكُمْ ۗ
وَلَيَزِيدَنَّ كَثِيرًا مِّنْهُم مَّآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ طُغْيَٰنًا وَكُفْرًا ۖ
فَلَا تَأْسَ عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٦٨﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَٱلَّذِينَ
هَادُوا۟ وَٱلصَّٰبِـُٔونَ وَٱلنَّصَٰرَىٰ مَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْـَٔاخِرِ
وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٦٩﴾ لَقَدْ أَخَذْنَا
مِيثَٰقَ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ وَأَرْسَلْنَآ إِلَيْهِمْ رُسُلًا ۖ كُلَّمَا جَآءَهُمْ رَسُولٌۢ
بِمَا لَا تَهْوَىٰٓ أَنفُسُهُمْ فَرِيقًا كَذَّبُوا۟ وَفَرِيقًا يَقْتُلُونَ ﴿٧٠﴾

(65) Kuma in da a ce waɗanda aka bai wa Littafi sun yi imani, kuma sun kiyaye dokokin Allah, to lalle da Mun kankare musu zunubansu, kuma lalle da Mun shigar da su gidajen Aljanna na ni'ima

(66) Kuma da a ce sun tsaya a kan aiki da Attaura da Linjila da kuma abin da aka saukar musu daga Ubangijinsu, lalle da sun ci daga samansu da kuma ƙarƙashin ƙafafunsu. Daga cikinsu akwai wata al'umma madaidaiciya, (amma) kuma mafi yawa daga cikinsu, irin abin da suke aikatawa ya munana (matuƙa)

(67) Ya kai wannan Manzo, ka isar da abin da aka saukar maka daga Ubangijinka; idan kuwa ba ka yi ba, to ba ka isar da saƙonsa ba. Allah kuwa Shi ne Yake kare ka daga (sharrin) mutane. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutanen da suke kafirai

(68) Ka ce: "Ya ku Ma'abota Littafi, ba kwa kan wani abu (na addinin gaskiya), har sai kun tsaya a kan yin aiki da Attaura da Linjila da kuma abin da aka saukar muku daga wajen Ubangijinku." Kuma abin da ake saukar maka daga Ubangijinka tabbas yana ƙara wa yawancinsu shisshigi da kafirci. Don haka kada ka yi baƙin ciki dangane da (abin da yake samun) mutane kafirai

(69) Lalle waɗanda suka yi imani da waɗanda suke Yahudawa da Sabi'awa da Nasara, duk wanda ya yi imani da Allah da ranar ƙarshe, kuma ya yi aiki nagari, to babu jin tsoro a tattare da su, kuma ba za su yi baƙin

(70) Lalle haƙiƙa Mun ɗauki alƙawari daga Bani-Isra'ila, kuma Muka aika musu da manzanni. Duk sa'adda wani manzo ya zo musu da abin da zukatansu ba sa so, sai su ƙaryata waɗansu kuma su riƙa kashe waɗansu

وَحَسِبُوٓاْ أَلَّا تَكُونَ فِتۡنَةٞ فَعَمُواْ وَصَمُّواْ ثُمَّ تَابَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡ ثُمَّ
عَمُواْ وَصَمُّواْ كَثِيرٞ مِّنۡهُمۡۚ وَٱللَّهُ بَصِيرُۢ بِمَا يَعۡمَلُونَ ٧١
لَقَدۡ كَفَرَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡمَسِيحُ ٱبۡنُ مَرۡيَمَۖ وَقَالَ ٱلۡمَسِيحُ
يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبَّكُمۡۖ إِنَّهُۥ مَن يُشۡرِكۡ
بِٱللَّهِ فَقَدۡ حَرَّمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِ ٱلۡجَنَّةَ وَمَأۡوَىٰهُ ٱلنَّارُۖ وَمَا
لِلظَّٰلِمِينَ مِنۡ أَنصَارٖ ٧٢ لَّقَدۡ كَفَرَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ
ثَالِثُ ثَلَٰثَةٖۘ وَمَا مِنۡ إِلَٰهٍ إِلَّآ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۚ وَإِن لَّمۡ يَنتَهُواْ
عَمَّا يَقُولُونَ لَيَمَسَّنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٌ ٧٣
أَفَلَا يَتُوبُونَ إِلَى ٱللَّهِ وَيَسۡتَغۡفِرُونَهُۥۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٧٤
مَّا ٱلۡمَسِيحُ ٱبۡنُ مَرۡيَمَ إِلَّا رَسُولٞ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِهِ ٱلرُّسُلُۖ وَأُمُّهُۥ
صِدِّيقَةٞۖ كَانَا يَأۡكُلَانِ ٱلطَّعَامَۗ ٱنظُرۡ كَيۡفَ نُبَيِّنُ لَهُمُ ٱلۡأٓيَٰتِ
ثُمَّ ٱنظُرۡ أَنَّىٰ يُؤۡفَكُونَ ٧٥ قُلۡ أَتَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا
يَمۡلِكُ لَكُمۡ ضَرّٗا وَلَا نَفۡعٗاۚ وَٱللَّهُ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٧٦ قُلۡ
يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ لَا تَغۡلُواْ فِي دِينِكُمۡ غَيۡرَ ٱلۡحَقِّ وَلَا تَتَّبِعُوٓاْ أَهۡوَآءَ
قَوۡمٖ قَدۡ ضَلُّواْ مِن قَبۡلُ وَأَضَلُّواْ كَثِيرٗا وَضَلُّواْ عَن سَوَآءِ ٱلسَّبِيلِ ٧٧

(71) Kuma sun zaci cewa, babu wata fitina da za ta auku, sai suka makance kuma suka kurumce, sannan Allah Ya karbi tubansu, sannan kuma da yawa daga cikinsu suka sake makancewa da kurumcewa. Allah kuma Mai ganin abin da suke aikatawa ne

(72) Lalle haƙiƙa waɗanda suka ce: "Lalle Allah Shi ne Almasihu ɗan Maryamu" sun kafirta. Shi kuwa Almasihu cewa ya yi: "Ya ku Bani-Isra'ila, ku bauta wa Allah Ubangijina kuma Ubangijinku. Lalle yadda al'amarin yake, duk wanda ya yi shirka da Allah, to haƙiƙa Allah Ya haramta masa shiga Aljanna, kuma makomarsa ita ce wuta, kuma azzalumai ba su da wasu mataimaka."

(73) Lalle haƙiƙa waɗannan da suka ce: "Lalle Allah Shi ne na cikon (alloli) uku,"[1] sun kafirta. Babu kuwa wani abin bautawa na gaskiya, sai abin bauta Daya tal. Idan ba su bar abin da suke faɗa ɗin nan ba, lalle azaba mai raɗaɗi za ta shafi waɗanda suka kafirta daga cikinsu

(74) Shin yanzu ba za su tuba zuwa ga Allah ba, kuma su nemi gafararsa? Allah kuwa Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(75) Shi fa Almasihu ɗan Maryamu bai zamo ba face Manzo, wanda haƙiƙa manzanni sun shuɗe kafinsa. Mahaifiyarsa kuma Siddiƙa ce; shi da ita sun kasance suna cin abinci. Duba ka ga yadda Muke bayyana musu ayoyi, sannan ka sake dubawa, ta yaya ake kautar da su?

(76) Ka ce: "Shin yanzu kwa riƙa bauta wa wani ba Allah ba, wanda ba ya mallakar cutarwa ko amfanarwa a gare ku; Shi kuwa Allah Shi ne Mai ji, kuma Masani?"

(77) Ka ce: "Ya ku ma'abota Littafi, kada ku zurfafa a ckin lamarin addiniku (ku ƙara) abin da ba gaskiya ba, kuma kada ku bi soye-soyen zukatan waɗansu mutanen da suka riga suka ɓata tun a da can, kuma sun ɓatar da mutane da yawa, kuma sun ɓace daga madaidaiciyar hanya."

(1) Ana nufin aƙidar Nasara da suke cewa, abu uku ne suka haɗu suka zama Allah, watau Isa da mahaifiyarsa Maryamu da kuma Allah.

لُعِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنۢ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ عَلَىٰ لِسَانِ
دَاوُۥدَ وَعِيسَى ٱبْنِ مَرْيَمَ ۚ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَوا۟ وَّكَانُوا۟
يَعْتَدُونَ ﴿٧٨﴾ كَانُوا۟ لَا يَتَنَاهَوْنَ عَن مُّنكَرٍ فَعَلُوهُ ۚ
لَبِئْسَ مَا كَانُوا۟ يَفْعَلُونَ ﴿٧٩﴾ تَرَىٰ كَثِيرًا مِّنْهُمْ
يَتَوَلَّوْنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ۚ لَبِئْسَ مَا قَدَّمَتْ لَهُمْ
أَنفُسُهُمْ أَن سَخِطَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمْ وَفِى ٱلْعَذَابِ هُمْ
خَٰلِدُونَ ﴿٨٠﴾ وَلَوْ كَانُوا۟ يُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلنَّبِىِّ وَمَآ
أُنزِلَ إِلَيْهِ مَا ٱتَّخَذُوهُمْ أَوْلِيَآءَ وَلَٰكِنَّ كَثِيرًا
مِّنْهُمْ فَٰسِقُونَ ﴿٨١﴾ ۞ لَتَجِدَنَّ أَشَدَّ ٱلنَّاسِ عَدَٰوَةً
لِّلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱلْيَهُودَ وَٱلَّذِينَ أَشْرَكُوا۟ ۖ وَلَتَجِدَنَّ
أَقْرَبَهُم مَّوَدَّةً لِّلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱلَّذِينَ قَالُوٓا۟ إِنَّا نَصَٰرَىٰ ۚ
ذَٰلِكَ بِأَنَّ مِنْهُمْ قِسِّيسِينَ وَرُهْبَانًا وَأَنَّهُمْ
لَا يَسْتَكْبِرُونَ ﴿٨٢﴾ وَإِذَا سَمِعُوا۟ مَآ أُنزِلَ إِلَى
ٱلرَّسُولِ تَرَىٰٓ أَعْيُنَهُمْ تَفِيضُ مِنَ ٱلدَّمْعِ مِمَّا عَرَفُوا۟
مِنَ ٱلْحَقِّ ۖ يَقُولُونَ رَبَّنَآ ءَامَنَّا فَٱكْتُبْنَا مَعَ ٱلشَّٰهِدِينَ ﴿٨٣﴾

(78) An la'anci waɗanda suka kafirta daga cikin Bani-Isra'ila a bisa harshen Dawuda da kuma Isa ɗan Maryamu. Hakan kuwa saboda abin da suka rika yi ne na saɓo, kuma sun kasance suna ƙetare iyaka
(79) Sun kasance ba sa hana junansu wani mummunan aikin da suka yi. Lalle tir da irin abin da suka kasance suna aikatawa
(80) Za ka ga yawancinsu suna nuna ƙauna ga waɗanda suka kafirta. Lalle tir da irin abin da kawunansu suka gabatar, don kuwa Allah Ya yi fushi da su, kuma su masu dawwama ne cikin azaba
(81) Kuma da sun kasance suna imani da Allah da Annabi da abin da aka saukar masa, da ba su rike su a matsayin masoya ba, sai dai kuma yawancinsu fasiƙai ne
(82) Tabbas lalle za ka samu cewa, mutanen da suka fi tsananin gaba da waɗanda suka yi imani, su ne Yahudawa da waɗanda suke mushirikai. Kuma tabbas lalle za ka sami waɗanda suka fi kusanci wajen nuna ƙauna ga waɗanda suka yi imani, su ne waɗanda suka ce: "Lalle mu Nasara ne." Wannan kuwa saboda a cikinsu akwai malamai da masu yawan ibada, don kuma lalle su ba sa yin girman kai
(83) Kuma idan sun ji abin da aka saukar wa wannan Manzo, za ka ga idanunsu suna zubar da hawaye, saboda abin da suka gane na gaskiya; suna cewa: "Ya Ubangijinmu, mun yi imani, don haka Ka rubuta mu cikin masu shaidawa

وَمَا لَنَا لَا نُؤْمِنُ بِاللَّهِ وَمَا جَاءَنَا مِنَ الْحَقِّ وَنَطْمَعُ أَن يُدْخِلَنَا
رَبُّنَا مَعَ الْقَوْمِ الصَّالِحِينَ ﴿٨٤﴾ فَأَثَابَهُمُ اللَّهُ بِمَا قَالُوا جَنَّاتٍ
تَجْرِي مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ خَالِدِينَ فِيهَا ۚ وَذَٰلِكَ جَزَاءُ
الْمُحْسِنِينَ ﴿٨٥﴾ وَالَّذِينَ كَفَرُوا وَكَذَّبُوا بِآيَاتِنَا أُولَٰئِكَ
أَصْحَابُ الْجَحِيمِ ﴿٨٦﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا لَا تُحَرِّمُوا
طَيِّبَاتِ مَا أَحَلَّ اللَّهُ لَكُمْ وَلَا تَعْتَدُوا ۚ إِنَّ اللَّهَ لَا يُحِبُّ
الْمُعْتَدِينَ ﴿٨٧﴾ وَكُلُوا مِمَّا رَزَقَكُمُ اللَّهُ حَلَالًا طَيِّبًا ۚ
وَاتَّقُوا اللَّهَ الَّذِي أَنتُم بِهِ مُؤْمِنُونَ ﴿٨٨﴾ لَا يُؤَاخِذُكُمُ اللَّهُ
بِاللَّغْوِ فِي أَيْمَانِكُمْ وَلَٰكِن يُؤَاخِذُكُم بِمَا عَقَّدتُّمُ الْأَيْمَانَ ۖ
فَكَفَّارَتُهُ إِطْعَامُ عَشَرَةِ مَسَاكِينَ مِنْ أَوْسَطِ مَا تُطْعِمُونَ
أَهْلِيكُمْ أَوْ كِسْوَتُهُمْ أَوْ تَحْرِيرُ رَقَبَةٍ ۖ فَمَن لَّمْ يَجِدْ فَصِيَامُ
ثَلَاثَةِ أَيَّامٍ ۚ ذَٰلِكَ كَفَّارَةُ أَيْمَانِكُمْ إِذَا حَلَفْتُمْ ۚ وَاحْفَظُوا
أَيْمَانَكُمْ ۚ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ اللَّهُ لَكُمْ آيَاتِهِ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿٨٩﴾
يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا إِنَّمَا الْخَمْرُ وَالْمَيْسِرُ وَالْأَنصَابُ وَالْأَزْلَامُ
رِجْسٌ مِّنْ عَمَلِ الشَّيْطَانِ فَاجْتَنِبُوهُ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿٩٠﴾

(84) "Kuma me muke da shi da ba za mu yi imani da Allah da abin da ya zo mana na gaskiya ba, muna kuwa sa rai Ubangijinmu Ya shigar da mu cikin salihan bayi?"
(85) Sai Allah Ya saka musu saboda abin da suka faɗa, da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dauwama a cikinsu, kuma wannan shi ne sakamakon masu kyautatawa
(86) Waɗanda kuwa suka kafirta, kuma suka ƙaryata ayoyinmu, waɗannan su ne 'yan wuta

(87) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku haramta kyawawan abubuwan da Allah Ya halatta muku, kuma kada ku ƙetare iyaka. Lalle Allah ba Ya son masu ƙetare iyaka
(88) Kuma ku ci daga abin da Allah Ya arzuta ku da shi, wanda yake halal, mai daɗi. Kuma ku kiyaye dokokin Allah Wanda kuke yin imani da Shi
(89) Allah ba zai kama ku da yasassun rantse-rantsenku ba[1], sai dai Yana kama ku ne da laifin abin da kuka ƙudurce na rantsuwa[2]; to kaffararsa ita ce ciyar da miskinai goma daga matsakaicin abin da kuke ciyar da iyalinku ko kuma tufatar da su ko 'yantar da bawa; wanda kuwa bai sami iko ba, to sai ya yi azumin kwana uku. Wannan shi ne kaffarar rantsuwarku, in kun yi rantsuwa. Kuma ku kiyaye rantse-rantsenku. Kamar haka ne Allah Yake bayyana muku ayoyinsa don ku zamo masu godiya
(90) Ya ku waɗanda suka yi imani, ita dai giya da caca da gumaka da kibau na neman sa'a[3], ba komai ba ne face ƙazanta daga aikin Shaiɗan, don haka ku nisance su domin ku sami rabauta.[4]

(1) Yasasshiyar rantsuwa ita ce rantsuwar da mutum yake yi ba da niyya ba.

(2) Watau yana kama mutum da rantsuwar da ya ƙudurci niyya a kanta.

(3) A jahiliyya balarabe idan zai yi tafiya ko zai yi wani aiki, sai ya ɗauko wasu kibiyoyi uku, ɗaya an rubuta 'aikata', ɗaya kuma 'kada ka aikata', ta uku kuma ba a rubuta komai a kanta ba, sai ya karkaɗa su sannan ya zaɓi ɗaya don ya gane sa'arsa ko rashinta.

(4) Da wannan ayar Allah ( ) ya haramta wa Musulmi shan giya da kasuwancinta.

إِنَّمَا يُرِيدُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَن يُوقِعَ بَيۡنَكُمُ ٱلۡعَدَٰوَةَ وَٱلۡبَغۡضَآءَ
فِي ٱلۡخَمۡرِ وَٱلۡمَيۡسِرِ وَيَصُدَّكُمۡ عَن ذِكۡرِ ٱللَّهِ وَعَنِ
ٱلصَّلَوٰةِۖ فَهَلۡ أَنتُم مُّنتَهُونَ ٩١ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ
ٱلرَّسُولَ وَٱحۡذَرُواْۚ فَإِن تَوَلَّيۡتُمۡ فَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَا عَلَىٰ رَسُولِنَا
ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ٩٢ لَيۡسَ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
جُنَاحٞ فِيمَا طَعِمُوٓاْ إِذَا مَا ٱتَّقَواْ وَّءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
ثُمَّ ٱتَّقَواْ وَّءَامَنُواْ ثُمَّ ٱتَّقَواْ وَّأَحۡسَنُواْۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ
ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٩٣ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَيَبۡلُوَنَّكُمُ ٱللَّهُ بِشَيۡءٖ
مِّنَ ٱلصَّيۡدِ تَنَالُهُۥٓ أَيۡدِيكُمۡ وَرِمَاحُكُمۡ لِيَعۡلَمَ ٱللَّهُ مَن يَخَافُهُۥ
بِٱلۡغَيۡبِۚ فَمَنِ ٱعۡتَدَىٰ بَعۡدَ ذَٰلِكَ فَلَهُۥ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٩٤ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقۡتُلُواْ ٱلصَّيۡدَ وَأَنتُمۡ حُرُمٞۚ وَمَن قَتَلَهُۥ
مِنكُم مُّتَعَمِّدٗا فَجَزَآءٞ مِّثۡلُ مَا قَتَلَ مِنَ ٱلنَّعَمِ يَحۡكُمُ بِهِۦ ذَوَا
عَدۡلٖ مِّنكُمۡ هَدۡيَۢا بَٰلِغَ ٱلۡكَعۡبَةِ أَوۡ كَفَّٰرَةٞ طَعَامُ مَسَٰكِينَ
أَوۡ عَدۡلُ ذَٰلِكَ صِيَامٗا لِّيَذُوقَ وَبَالَ أَمۡرِهِۦۗ عَفَا ٱللَّهُ عَمَّا
سَلَفَۚ وَمَنۡ عَادَ فَيَنتَقِمُ ٱللَّهُ مِنۡهُۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٞ ذُو ٱنتِقَامٖ ٩٥

(91) Abin da kawai Shaiɗan yake nufi shi ne, ya jefa gaba da ƙiyayya a tsakankaninku, ta hanyar giya da caca, kuma ya hana muku ambaton Allah da yin salla. Shin ko kun hanu?

(92) Kuma ku bi Allah, kuma ku bi wannan Manzon, kuma ku yi hattara. Idan kuka juya baya, to ku sani abin da kawai yake kan Manzonmu shi ne isar da saƙo filla-filla

(93) Babu wani laifi a kan waɗanda suka yi imani, kuma suka yi aiki nagari cikin abin da suka taɓa sha (na giya a baya), in dai sun yi taƙawa, kuma sun yi imani, kuma sun aikata aiki nagari, sannan suka yi taƙawa da imani, sannan suka yi taƙawa kuma suka kyautata. Kuma Allah Yana son masu kyautatawa

(94) Ya ku waɗanda suka yi imani, lalle Allah zai jarrabe ku da wani abu na farauta, wanda hannayenku da masunku za su kai gare shi, don Allah Ya bayyana wanda yake jin tsoron Sa alhalin bai gan Shi ba. Don haka duk wanda ya ƙetare iyaka bayan haka, to lalle yana da azaba mai raɗaɗi

(95) ¡Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku kashe abin farauta alhali kuna cikin Harami[1]. Duk kuwa wanda ya kashe shi daga cikinku da gangan, to sakamakonsa shi ne (ya bayar) da kwatankwacin abin da ya kashe cikin dabbobin gida; waɗanda za su yi hukunci da wannan su ne mutum biyu adalai a cikinku, a matsayin hadaya wadda za ta isa Ka'aba, ko kuma ya yi kaffarar ciyar da miskinai, ko kuma ya yi azumi na kwatankwacin haka, don ya ɗanɗani kuɗar lamarinsa. Allah Ya yi afuwa dangane da abin da ya wuce. Duk kuwa wanda ya sake komawa, to Allah zai yi masa uƙuba. Kuma Allah Mabuwayi ne, Ma'abocin uƙuba

(1) Watau kuna sanye da haramin hajji ko na umara.

أُحِلَّ لَكُمْ صَيْدُ ٱلْبَحْرِ وَطَعَامُهُۥ مَتَٰعًا لَّكُمْ وَلِلسَّيَّارَةِ ۖ
وَحُرِّمَ عَلَيْكُمْ صَيْدُ ٱلْبَرِّ مَا دُمْتُمْ حُرُمًا ۗ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ٱلَّذِىٓ
إِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ﴿٩٦﴾ جَعَلَ ٱللَّهُ ٱلْكَعْبَةَ ٱلْبَيْتَ ٱلْحَرَامَ
قِيَٰمًا لِّلنَّاسِ وَٱلشَّهْرَ ٱلْحَرَامَ وَٱلْهَدْىَ وَٱلْقَلَٰٓئِدَ ۚ ذَٰلِكَ لِتَعْلَمُوٓا۟
أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ وَأَنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ
شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿٩٧﴾ ٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ وَأَنَّ ٱللَّهَ
غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٩٨﴾ مَّا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلْبَلَٰغُ ۗ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ مَا
تُبْدُونَ وَمَا تَكْتُمُونَ ﴿٩٩﴾ قُل لَّا يَسْتَوِى ٱلْخَبِيثُ وَٱلطَّيِّبُ
وَلَوْ أَعْجَبَكَ كَثْرَةُ ٱلْخَبِيثِ ۚ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ يَٰٓأُو۟لِى ٱلْأَلْبَٰبِ
لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿١٠٠﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَسْـَٔلُوا۟ عَنْ
أَشْيَآءَ إِن تُبْدَ لَكُمْ تَسُؤْكُمْ وَإِن تَسْـَٔلُوا۟ عَنْهَا حِينَ يُنَزَّلُ
ٱلْقُرْءَانُ تُبْدَ لَكُمْ عَفَا ٱللَّهُ عَنْهَا ۗ وَٱللَّهُ غَفُورٌ حَلِيمٌ ﴿١٠١﴾
قَدْ سَأَلَهَا قَوْمٌ مِّن قَبْلِكُمْ ثُمَّ أَصْبَحُوا۟ بِهَا كَٰفِرِينَ ﴿١٠٢﴾ مَا جَعَلَ
ٱللَّهُ مِنۢ بَحِيرَةٍ وَلَا سَآئِبَةٍ وَلَا وَصِيلَةٍ وَلَا حَامٍ وَلَٰكِنَّ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ يَفْتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ ۖ وَأَكْثَرُهُمْ لَا يَعْقِلُونَ ﴿١٠٣﴾

(96) An halatta muku yin farautar naman ruwa da abincin cikinsa[1], don jin dadi a gare ku da kuma matafiya; amma an haramta muku farautar naman daji matukar kuna cikin Harami. Kuma ku kiyaye dokokin Allah Wanda zuwa gare Shi za a tattara ku

(97) Allah Ya sanya Ka'aba ɗaki ne mai alfarma, wuri mai matuƙar amfani ga mutane, haka watanni masu alfarma, da dabbar hadaya da dabbar hadaya mai rataye. Wannan kuwa don ku sani cewa, lalle Allah Ya san abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa, kuma lalle Allah Masanin komai ne

(98) Ku sani lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne, kuma lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(99) Babu abin da yake kan Manzo sai isarwa. Kuma Allah Yana sane da abin da kuke bayyanawa da abin da kuke ɓoyewa

(100) Ka ce: "Mummuna da kyakkyawa ba za su taɓa zama daidai ba, ko da kuwa yawan mummunan ya burge ka." Don haka ku kiyaye dokokin Allah, ya ku ma'abota hankali, don ku sami rabauta

(101) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku yi tambaya game da waɗansu al'amurra, waɗanda idan aka bayyana muku su za su dame ku, idan kuwa kuka rifka tambaya game da su yayin da Alƙur'ani yake sauka, za a bayyana muku su; Allah Ya yi rangwame game da su. Kuma Allah Mai gafara ne, Mai haƙuri

(102) Haƙiƙa waɗansu mutane gabaninku sun yi irin wannan tambayar, sannan suka wayi gari suna kafirce mata

(103) Allah bai sanya wata dabba bahîra ba ko sá'iba ko wasîla ko hám[2] ba, sai dai waɗanda suka kafirta suna ƙirƙirar ƙarya su jingina wa Allah; kuma yawancinsu ba sa hankalta

(1) Watau abin da kogi ya yi ambaliyar sa an halatta wa waɗanda suke cikin haramin hajji ko umara farautar sa da cin sa.

(2) Bahîra da sá'iba da wasîla da hám duk waɗannan dabbobi ne da mushirikan Laraba-wa suke 'yanta su ga gumakansu, ba a hawan su, ba a ɗora musu kaya, ba a cin namansu.

وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ تَعَالَوْا۟ إِلَىٰ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ وَإِلَى ٱلرَّسُولِ قَالُوا۟ حَسْبُنَا
مَا وَجَدْنَا عَلَيْهِ ءَابَآءَنَآ ۚ أَوَلَوْ كَانَ ءَابَآؤُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ
شَيْـًٔا وَلَا يَهْتَدُونَ ﴿١٠٤﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ عَلَيْكُمْ أَنفُسَكُمْ ۖ
لَا يَضُرُّكُم مَّن ضَلَّ إِذَا ٱهْتَدَيْتُمْ ۚ إِلَى ٱللَّهِ مَرْجِعُكُمْ جَمِيعًا
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿١٠٥﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ شَهَٰدَةُ
بَيْنِكُمْ إِذَا حَضَرَ أَحَدَكُمُ ٱلْمَوْتُ حِينَ ٱلْوَصِيَّةِ ٱثْنَانِ ذَوَا
عَدْلٍ مِّنكُمْ أَوْ ءَاخَرَانِ مِنْ غَيْرِكُمْ إِنْ أَنتُمْ ضَرَبْتُمْ فِى ٱلْأَرْضِ
فَأَصَٰبَتْكُم مُّصِيبَةُ ٱلْمَوْتِ ۚ تَحْبِسُونَهُمَا مِنۢ بَعْدِ ٱلصَّلَوٰةِ
فَيُقْسِمَانِ بِٱللَّهِ إِنِ ٱرْتَبْتُمْ لَا نَشْتَرِى بِهِۦ ثَمَنًا وَلَوْ كَانَ ذَا
قُرْبَىٰ وَلَا نَكْتُمُ شَهَٰدَةَ ٱللَّهِ إِنَّآ إِذًا لَّمِنَ ٱلْءَاثِمِينَ ﴿١٠٦﴾ فَإِنْ عُثِرَ
عَلَىٰٓ أَنَّهُمَا ٱسْتَحَقَّآ إِثْمًا فَـَٔاخَرَانِ يَقُومَانِ مَقَامَهُمَا مِنَ ٱلَّذِينَ
ٱسْتَحَقَّ عَلَيْهِمُ ٱلْأَوْلَيَٰنِ فَيُقْسِمَانِ بِٱللَّهِ لَشَهَٰدَتُنَآ أَحَقُّ مِن
شَهَٰدَتِهِمَا وَمَا ٱعْتَدَيْنَآ ۖ إِنَّآ إِذًا لَّمِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٠٧﴾ ذَٰلِكَ أَدْنَىٰٓ
أَن يَأْتُوا۟ بِٱلشَّهَٰدَةِ عَلَىٰ وَجْهِهَآ أَوْ يَخَافُوٓا۟ أَن تُرَدَّ أَيْمَٰنٌۢ بَعْدَ
أَيْمَٰنِهِمْ ۗ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَٱسْمَعُوا۟ ۗ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْفَٰسِقِينَ ﴿١٠٨﴾

(104) Kuma idan aka ce da su: "Ku taho zuwa ga abin da Allah Ya saukar da kuma zuwa ga Manzo," sai su ce: "Abin da muka sami iyayenmu a kai ya ishe mu." Yanzu ko da iyayen nasu sun kasance ba su san komai ba, kuma ba sa shiryuwa?

(105) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi ta kanku; wanda ya ɓata, ba zai cutar da ku ba idan har ku kun shiryu. Zuwa ga Allah ne makomarku take gaba ɗaya, sannan kuma zai ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa

(106) Ya ku waɗanda suka yi imani, shaidar da take tsakaninku idan alamun mutuwa suka zo wa ɗaya daga cikinku, yayin da ya so ya yi wasiyya, shi ne a samu mutum biyu masu adalci daga cikinku ko kuma waɗansu biyu daga wasunku (kafirai), yayin da kuka yi tafiya a bayan ƙasa, sai musibar mutuwa ta same ku. Za ku tsayar da su (shaidun) biyun ne bayan an kammala salla, sai su rantse da Allah- idan har kun yi shakka game da su-: "Wallahi, ba za mu musanya shi da wani farashi ba, ko da kuwa ya zamo ma'abocin kusanci ne, kuma ba za mu ɓoye shaidar Allah ba, lalle kuwa idan har muka yi haka, tabbas muna cikin masu laifi."

(107) Amma idan an gano cewa su biyun sun yi laifi, sai a nemi mutum biyu su tsaya su yi shaida a madadin waɗancan daga cikin waɗanda suka cancanta su ci gadonsa, sai su rantse da Allah: "Wallahi, shaidarmu ta fi shaidarsu, kuma wallahi ba mu ƙetare iyaka ba, lalle kuwa idan mun yi haka, tabbas da mun zama cikin azzalumai."

(108) Yin haka shi ne ya fi kusa da su kawo shaida kamar yadda take, ko su ji tsoron a mayar da wannan shaidar bayan rantsuwarsu. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku saurari (umarninsa), kuma Allah ba Ya shiryar da mutanen da suke fasiƙai



يَوْمَ يَجْمَعُ ٱللَّهُ ٱلرُّسُلَ فَيَقُولُ مَاذَآ أُجِبْتُمْ ۖ قَالُوا۟ لَا عِلْمَ لَنَآ ۖ
إِنَّكَ أَنتَ عَلَّٰمُ ٱلْغُيُوبِ ﴿١٠٩﴾ إِذْ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ
ٱذْكُرْ نِعْمَتِى عَلَيْكَ وَعَلَىٰ وَٰلِدَتِكَ إِذْ أَيَّدتُّكَ بِرُوحِ
ٱلْقُدُسِ تُكَلِّمُ ٱلنَّاسَ فِى ٱلْمَهْدِ وَكَهْلًا ۖ وَإِذْ عَلَّمْتُكَ
ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ وَٱلتَّوْرَىٰةَ وَٱلْإِنجِيلَ ۖ وَإِذْ تَخْلُقُ
مِنَ ٱلطِّينِ كَهَيْـَٔةِ ٱلطَّيْرِ بِإِذْنِى فَتَنفُخُ فِيهَا فَتَكُونُ
طَيْرًۢا بِإِذْنِى ۖ وَتُبْرِئُ ٱلْأَكْمَهَ وَٱلْأَبْرَصَ بِإِذْنِى ۖ وَإِذْ تُخْرِجُ
ٱلْمَوْتَىٰ بِإِذْنِى ۖ وَإِذْ كَفَفْتُ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ عَنكَ إِذْ
جِئْتَهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنْهُمْ إِنْ هَٰذَآ
إِلَّا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿١١٠﴾ وَإِذْ أَوْحَيْتُ إِلَى ٱلْحَوَارِيِّـۧنَ أَنْ ءَامِنُوا۟
بِى وَبِرَسُولِى ۖ قَالُوٓا۟ ءَامَنَّا وَٱشْهَدْ بِأَنَّنَا مُسْلِمُونَ ﴿١١١﴾
إِذْ قَالَ ٱلْحَوَارِيُّونَ يَٰعِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ هَلْ يَسْتَطِيعُ رَبُّكَ
أَن يُنَزِّلَ عَلَيْنَا مَآئِدَةً مِّنَ ٱلسَّمَآءِ ۖ قَالَ ٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ إِن كُنتُم
مُّؤْمِنِينَ ﴿١١٢﴾ قَالُوا۟ نُرِيدُ أَن نَّأْكُلَ مِنْهَا وَتَطْمَئِنَّ قُلُوبُنَا
وَنَعْلَمَ أَن قَدْ صَدَقْتَنَا وَنَكُونَ عَلَيْهَا مِنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ﴿١١٣﴾

(109) (Ka tuna) ranar da Allah zai tara manzanni, sannan Ya ce: "Da me aka ba ku amsa?" sai su ce: "Ba mu da wata masaniya; lalle Kai ne kaɗai Masanin abubuwan da suke ɓoye."

(110) (Ka tuna) lokacin da Allah zai ce: "Ya kai Isa ɗan Maryamu, ka tuna ni'imata da Na yi maka kai da mahaifiyarka, yayin da Na ƙarfafe ka da Ruhi mai tsarki, kana yi wa mutane magana lokacin kana cikin zanin goyo, da kuma lokacin da kake dattijo, kuma ka tuna lokacin da Na koyar da kai rubutu da hikima da Attaura da Linjila. Kuma ka tuna lokacin da kake ƙirƙirar (wani abu) kamar tsuntsu da taɓo da izinina, sai ka yi busa a cikinsa, sai ya zamo tsuntsu da izinina; kuma kake warkar da wanda aka haifa da makanta da mai albaras da izinina; kuma ka tuna lokacin da kake fito da matattu (daga cikin ƙaburburansu) da izinina; kuma ka tuna lokacin da Na kare ka (daga cutar) Bani Isra'ila yayin da ka zo musu da hujjoji bayyanannu, sai waɗanda suka kafirta daga cikinsu suka ce: "Ai wannan ba komai ba ne face sihiri mabayyani."

(111) Kuma ka tuna lokacin da Na yi wahayi zuwa ga Hawariyyawa: "Ku yi imani da Ni da Manzona," sai suka ce: "Mun yi imani, kuma Ka shaida cewa, mu Musulmai ne."

(112) Lokacin da Hawariyyawa suka ce: "Ya Isa ɗan Maryamu, shin Ubangijinka Yana iya saukar mana da kaɓaki daga sama?" Ya ce: "Ku kiyayi Allah, idan har kun kasance muminai."

(113) Suka ce: "Mu muna nufin mu ci daga gare shi, kuma zukatanmu su sami nutsuwa, sannan mu haƙiƙance cewa, lalle ka faɗa mana gaskiya, kuma mu zamo masu ba da shaida a kansa."

قَالَ عِيسَى ٱبْنُ مَرْيَمَ ٱللَّهُمَّ رَبَّنَآ أَنزِلْ عَلَيْنَا مَآئِدَةً مِّنَ ٱلسَّمَآءِ
تَكُونُ لَنَا عِيدًا لِّأَوَّلِنَا وَءَاخِرِنَا وَءَايَةً مِّنكَ ۖ وَٱرْزُقْنَا وَأَنتَ
خَيْرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ﴿١١٤﴾ قَالَ ٱللَّهُ إِنِّى مُنَزِّلُهَا عَلَيْكُمْ ۖ فَمَن يَكْفُرْ بَعْدُ
مِنكُمْ فَإِنِّىٓ أُعَذِّبُهُۥ عَذَابًا لَّآ أُعَذِّبُهُۥٓ أَحَدًا مِّنَ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١١٥﴾
وَإِذْ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ ءَأَنتَ قُلْتَ لِلنَّاسِ ٱتَّخِذُونِى
وَأُمِّىَ إِلَٰهَيْنِ مِن دُونِ ٱللَّهِ ۖ قَالَ سُبْحَٰنَكَ مَا يَكُونُ لِىٓ أَنْ أَقُولَ
مَا لَيْسَ لِى بِحَقٍّ ۚ إِن كُنتُ قُلْتُهُۥ فَقَدْ عَلِمْتَهُۥ ۚ تَعْلَمُ مَا فِى نَفْسِى
وَلَآ أَعْلَمُ مَا فِى نَفْسِكَ ۚ إِنَّكَ أَنتَ عَلَّٰمُ ٱلْغُيُوبِ ﴿١١٦﴾ مَا قُلْتُ لَهُمْ
إِلَّا مَآ أَمَرْتَنِى بِهِۦٓ أَنِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ رَبِّى وَرَبَّكُمْ ۚ وَكُنتُ عَلَيْهِمْ
شَهِيدًا مَّا دُمْتُ فِيهِمْ ۖ فَلَمَّا تَوَفَّيْتَنِى كُنتَ أَنتَ ٱلرَّقِيبَ عَلَيْهِمْ ۚ
وَأَنتَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ شَهِيدٌ ﴿١١٧﴾ إِن تُعَذِّبْهُمْ فَإِنَّهُمْ عِبَادُكَ ۖ وَإِن
تَغْفِرْ لَهُمْ فَإِنَّكَ أَنتَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿١١٨﴾ قَالَ ٱللَّهُ هَٰذَا يَوْمُ يَنفَعُ
ٱلصَّٰدِقِينَ صِدْقُهُمْ ۚ لَهُمْ جَنَّٰتٌ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ
فِيهَآ أَبَدًا ۖ رَّضِىَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ ۚ ذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿١١٩﴾ لِلَّهِ
مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا فِيهِنَّ ۚ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿١٢٠﴾

(114) Isa ɗan Maryamu ya ce: "Ya Allah Ubangijinmu, Ka saukar mana da kaɓaki daga sama, wanda zai zame mana wani Idi, ga na farkonmu da na ƙarshenmu, kuma ya zamo wata aya daga gare Ka; kuma Ka arzuta mu, lalle Kai ne Fiyayyen masu arzutawa."

(115) Allah Ya ce: "Lalle Ni Mai saukar muku da shi (kaɓakin) ne; amma duk wanda ya kafirta daga baya cikinku, to lalle Ni zan yi masa wata irin azaba wadda ba zan taɓa azabtar da wani daga cikin halittu irinta ba."

(116) Kuma (ka tuna) lokacin da Allah zai ce: "Ya kai Isa ɗan Maryamu, shin kai ne ka ce da mutane: 'Ku riƙe ni, ni da mahaifiyata a matsayin alloli biyu ban da Allah?'" Sai ya ce: "Tsarki ya tabbata gare Ka, bai dace ba a gare ni in faɗi wani abu wanda ba ni da haƙƙin (faɗar sa). Idan har na faɗe shi, to haƙiƙa Ka riga Ka sani, Ka san abin da yake cikin raina, amma ni ban san abin da yake ranka ba. Lalle Kai ne Masanin abubuwan da suke ɓoye

(117) "Ban faɗa musu komai ba sai abin da Ka umarce ni da shi, cewa: 'Ku bauta wa Allah Ubangijina, kuma Ubangijinku.' Kuma na kasance mai sa ido a kansu lokacin da nake cikinsu. Amma yayin da Ka karɓi rayuwata, Ka zama Kai ne Mai kula da su. Kuma lalle Kai Mai kula ne a kan komai

(118) "Idan har Ka azabtar da su, haƙiƙa su bayinka ne; idan kuwa Ka yafe musu, to lalle Kai Mabuwayi ne, Mai hikima."

(119) Allah zai ce: "Wannan ita ce rana wadda gaskiya za ta amfani masu ita. Suna da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za su dawwama a cikinsu har abada. Allah Ya yarda da su, su kuma sun yarda da Shi. Wannan shi ne rabo mai girma."

(120) Mulkin sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu na Allah ne. Kuma Shi Mai iko ne a kan komai

Sura An'am

سُورَةُ الأَنعَامِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَجَعَلَ ٱلظُّلُمَٰتِ
وَٱلنُّورَۖ ثُمَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِرَبِّهِمۡ يَعۡدِلُونَ ١ هُوَ ٱلَّذِي
خَلَقَكُم مِّن طِينٖ ثُمَّ قَضَىٰٓ أَجَلٗاۖ وَأَجَلٞ مُّسَمًّى عِندَهُۥۖ ثُمَّ أَنتُمۡ
تَمۡتَرُونَ ٢ وَهُوَ ٱللَّهُ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَفِي ٱلۡأَرۡضِ يَعۡلَمُ سِرَّكُمۡ
وَجَهۡرَكُمۡ وَيَعۡلَمُ مَا تَكۡسِبُونَ ٣ وَمَا تَأۡتِيهِم مِّنۡ ءَايَةٖ مِّنۡ
ءَايَٰتِ رَبِّهِمۡ إِلَّا كَانُواْ عَنۡهَا مُعۡرِضِينَ ٤ فَقَدۡ كَذَّبُواْ بِٱلۡحَقِّ
لَمَّا جَآءَهُمۡ فَسَوۡفَ يَأۡتِيهِمۡ أَنۢبَٰٓؤُاْ مَا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٥
أَلَمۡ يَرَوۡاْ كَمۡ أَهۡلَكۡنَا مِن قَبۡلِهِم مِّن قَرۡنٖ مَّكَّنَّٰهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ
مَا لَمۡ نُمَكِّن لَّكُمۡ وَأَرۡسَلۡنَا ٱلسَّمَآءَ عَلَيۡهِم مِّدۡرَارٗا وَجَعَلۡنَا ٱلۡأَنۡهَٰرَ
تَجۡرِي مِن تَحۡتِهِمۡ فَأَهۡلَكۡنَٰهُم بِذُنُوبِهِمۡ وَأَنشَأۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِمۡ قَرۡنًا
ءَاخَرِينَ ٦ وَلَوۡ نَزَّلۡنَا عَلَيۡكَ كِتَٰبٗا فِي قِرۡطَاسٖ فَلَمَسُوهُ بِأَيۡدِيهِمۡ
لَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِنۡ هَٰذَآ إِلَّا سِحۡرٞ مُّبِينٞ ٧ وَقَالُواْ لَوۡلَآ أُنزِلَ
عَلَيۡهِ مَلَكٞۖ وَلَوۡ أَنزَلۡنَا مَلَكٗا لَّقُضِيَ ٱلۡأَمۡرُ ثُمَّ لَا يُنظَرُونَ ٨

(1) Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Wanda Ya halicci sammai da ƙasa, kuma Ya halicci duffai da haske; sannan waɗanda suka kafirta suna daidaita Ubangijinsu da (wasu)
(2) Shi ne Wanda Ya halicce ku daga taɓo, sannan Ya yanka (muku) ajali; da kuma wani ajalin sananne a wurinsa; sannan sai ga shi kuna jayayya
(3) Kuma Shi ne Allah a cikin sammai da kuma cikin ƙasa; Yana sane da abin da kuke ɓoyewa da abin da kuke bayyanawa, kuma Yana sane da abin da kuke aikatawa
(4) Kuma babu wata aya cikin ayoyin Ubangijinsu da za ta zo musu, face sai sun kasance masu bijire mata
(5) To haƙiƙa sun ƙaryata gaskiya lokacin da ta zo musu; don haka da sannu labaran abin da suka kasance suna izgili da shi zai zo musu
(6) Shin ba su ga yawan al'ummun da Muka halakar a gabaninsu ba, waɗanda Muka kafa su a banƙasa suka yi ƙarfi irin kafawar da ba Mu yi muku ba[1] , kuma Muka aiko musu da ruwan sama a kai a kai, kuma Muka sanya ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu, sai Muka hallakar da su saboda zunubansu, kuma bayan shuɗewarsu Muka halicci wata sabuwar al'ummar daban?
(7) Kuma in da Mun saukar maka da wani littafin a rubuce a takardu, har suka taɓa shi da hannayensu, lalle da waɗanda suka kafirta sun ce: "Wannan ba komai ba ne, face sihiri bayyananne."
(8) Kuma suka ce: "Don me ba a saukar masa da mala'ika ba?" Da kuwa Mun saukar da mala'ikan, to da ta faru ta ƙare (an hallaka su), sannan ba za a saurara musu ba

(1) Allah ya ba su ƙarfin jiki da yawan dukiya da 'ya'ya. Dubi Suratur Rum aya ta 9-10 da Suratus Saba'i aya ta 45.

وَلَوْ جَعَلْنَٰهُ مَلَكًا لَّجَعَلْنَٰهُ رَجُلًا وَلَلَبَسْنَا عَلَيْهِم مَّا
يَلْبِسُونَ ﴿٩﴾ وَلَقَدِ ٱسْتُهْزِئَ بِرُسُلٍ مِّن قَبْلِكَ فَحَاقَ بِٱلَّذِينَ
سَخِرُوا۟ مِنْهُم مَّا كَانُوا۟ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿١٠﴾ قُلْ سِيرُوا۟
فِى ٱلْأَرْضِ ثُمَّ ٱنظُرُوا۟ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُكَذِّبِينَ
﴿١١﴾ قُل لِّمَن مَّا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ قُل لِّلَّهِ ۚ كَتَبَ عَلَىٰ
نَفْسِهِ ٱلرَّحْمَةَ ۚ لَيَجْمَعَنَّكُمْ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ لَا رَيْبَ
فِيهِ ۚ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ فَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿١٢﴾ ۞ وَلَهُۥ
مَا سَكَنَ فِى ٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ ۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ ﴿١٣﴾ قُلْ
أَغَيْرَ ٱللَّهِ أَتَّخِذُ وَلِيًّا فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَهُوَ
يُطْعِمُ وَلَا يُطْعَمُ ۗ قُلْ إِنِّىٓ أُمِرْتُ أَنْ أَكُونَ أَوَّلَ مَنْ أَسْلَمَ ۖ
وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿١٤﴾ قُلْ إِنِّىٓ أَخَافُ إِنْ عَصَيْتُ
رَبِّى عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿١٥﴾ مَّن يُصْرَفْ عَنْهُ يَوْمَئِذٍ فَقَدْ رَحِمَهُۥ ۚ
وَذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ ٱلْمُبِينُ ﴿١٦﴾ وَإِن يَمْسَسْكَ ٱللَّهُ بِضُرٍّ فَلَا كَاشِفَ
لَهُۥٓ إِلَّا هُوَ ۖ وَإِن يَمْسَسْكَ بِخَيْرٍ فَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ
﴿١٧﴾ وَهُوَ ٱلْقَاهِرُ فَوْقَ عِبَادِهِۦ ۚ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْخَبِيرُ ﴿١٨﴾

(9) Kuma in da Mun yo shi mala'ika ne, to lalle da Mun mayar da shi mutum, kuma da lalle Mun rikitar da su kamar yadda suka rikitar da kansu

(10) Kuma haƙiƙa an yi wa waɗansu manzanni da suka gabace ka izgili, sai sakamakon abin da suka kasance suna yin izgili da shi ya sauka kan masu izgilin

(11) Ka ce: "Ku yi tafiya a bayan ƙasa, sannan ku duba ku ga, yaya ƙarshen lamarin masu ƙaryatawa ya kasance?"

(12) Ka ce: "Abin da yake cikin sammai da ƙasa na wane ne?" Ka ce: "Na Allah ne." Ya wajabta wa kansa yin rahama. Lalle tabbas zai tattara ku zuwa ranar tashin alƙiyama wadda babu kokwanto game da ita. Waɗanda suka yi hasarar kawunansu ba za su yi imani ba

(13) "Kuma abin da ya nutsu a cikin dare ko rana nasa ne, kuma Shi ne Mai ji, Mai yawan sani."

(14) Ka ce: "Shin yanzu wanin Allah ne zan riƙa a matsayin majiɓinci, alhalin Shi ne Ya halicci sammai da ƙasa, kuma Shi Yake ciyarwa, ba a ciyar da Shi?" Ka ce: "Lalle ni an umarce ni da in zamo farkon mai miƙa wuya; kuma lalle kada ka kasance daga masu shirka."

(15) Ka ce: "Lalle ni ina jin tsoron azabar rana mai girma, idan na saba wa Ubangijina."

(16) Wanda duk aka kawar masa da (azaba) a wannan rana, to haƙiƙa (Allah) Ya ji ƙan sa. Kuma wannan Shi ne rabo mabayyani

(17) Kuma idan Allah Ya shafe ka da wata cuta, to ba wanda ya isa ya yaye ta sai Shi; kuma idan Ya shafe ka da wani alheri, to Shi Mai iko ne a kan komai

(18) Kuma Shi ne Mai rinjaye a kan bayinsa. Kuma Shi Mai hikima ne, Masani

قُلْ أَيُّ شَيْءٍ أَكْبَرُ شَهَٰدَةً ۖ قُلِ ٱللَّهُ ۖ شَهِيدٌۢ بَيْنِى وَبَيْنَكُمْ ۚ وَأُوحِىَ إِلَىَّ هَٰذَا
ٱلْقُرْءَانُ لِأُنذِرَكُم بِهِۦ وَمَنۢ بَلَغَ ۚ أَئِنَّكُمْ لَتَشْهَدُونَ أَنَّ مَعَ ٱللَّهِ ءَالِهَةً
أُخْرَىٰ ۚ قُل لَّآ أَشْهَدُ ۚ قُلْ إِنَّمَا هُوَ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ وَإِنَّنِى بَرِىٓءٌ مِّمَّا تُشْرِكُونَ
﴿١٩﴾ ٱلَّذِينَ ءَاتَيْنَٰهُمُ ٱلْكِتَٰبَ يَعْرِفُونَهُۥ كَمَا يَعْرِفُونَ أَبْنَآءَهُمُ ۘ ٱلَّذِينَ
خَسِرُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ فَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿٢٠﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى
ٱللَّهِ كَذِبًا أَوْ كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِهِۦٓ ۚ إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٢١﴾ وَيَوْمَ نَحْشُرُهُمْ
جَمِيعًا ثُمَّ نَقُولُ لِلَّذِينَ أَشْرَكُوٓا۟ أَيْنَ شُرَكَآؤُكُمُ ٱلَّذِينَ كُنتُمْ تَزْعُمُونَ ﴿٢٢﴾
ثُمَّ لَمْ تَكُن فِتْنَتُهُمْ إِلَّآ أَن قَالُوا۟ وَٱللَّهِ رَبِّنَا مَا كُنَّا مُشْرِكِينَ ﴿٢٣﴾
ٱنظُرْ كَيْفَ كَذَبُوا۟ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ ۚ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ﴿٢٤﴾
وَمِنْهُم مَّن يَسْتَمِعُ إِلَيْكَ ۖ وَجَعَلْنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ أَكِنَّةً أَن يَفْقَهُوهُ
وَفِىٓ ءَاذَانِهِمْ وَقْرًا ۖ وَإِن يَرَوْا۟ كُلَّ ءَايَةٍ لَّا يُؤْمِنُوا۟ بِهَا ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا
جَآءُوكَ يُجَٰدِلُونَكَ يَقُولُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ إِنْ هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ
ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٢٥﴾ وَهُمْ يَنْهَوْنَ عَنْهُ وَيَنْـَٔوْنَ عَنْهُ ۖ وَإِن يُهْلِكُونَ إِلَّآ
أَنفُسَهُمْ وَمَا يَشْعُرُونَ ﴿٢٦﴾ وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذْ وُقِفُوا۟ عَلَى ٱلنَّارِ فَقَالُوا۟
يَٰلَيْتَنَا نُرَدُّ وَلَا نُكَذِّبَ بِـَٔايَٰتِ رَبِّنَا وَنَكُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٢٧﴾

(19) Ka ce: "Mene ne mafi girman shaida?" Ka ce; "Allah Shi ne shaida tsakanina da ku. Kuma an saukar mini wannan Alkur'anin ne don in yi muku gargadi da shi da kuma duk wanda zai isa zuwa gare shi. Yanzu kuwa za ku shaida cewa, lalle akwai waɗansu allolin tare da Allah?" Ka ce: "Ni kam ba zan shaida ba." Ka ce: "Allah Shi Daya ne, kuma lalle ni ba ruwana da dukkan abin da kuke haɗa Allah da shi."

(20) Waɗanda Muka ba su Littafi sun san shi kamar yadda suka san 'ya'yansu. Waɗanda suka yi hasarar kawunansu, to su kam ba za su taɓa yin imani ba

(21) Kuma ba mafi zalunci fiye da wanda ya ƙirƙiri ƙarya ya jingina wa Allah, ko kuma ya ƙaryata ayoyinsa. Haƙiƙar lamarin dai su azzalumai ba za su taɓa rabauta ba

(22) Kuma (ka tuna) ranar da za Mu tattara su gaba ɗaya, sannan Mu ce da waɗanda suka yi shirka: "Ina abokan tarayyarku waɗanda kuka kasance kuna riyawa?"

(23) Sannan fitinarsu ba ta zamo komai ba, face cewar da suka yi: "Wallahi, ya Ubangijinmu, ba mu kasance masu yin shirka ba!"

(24) Duba ka ga yadda suka yi wa kansu ƙarya. Kuma abin da suka kasance suna ƙirƙira ya ɓace musu

(25) Kuma daga cikinsu akwai wanda yake sauraren ka; kuma Mun sanya murafai a zukatansu, ta yadda ba za su iya fahimtar sa ba, haka kuma a kunnuwansu akwai wata toshiya. Kuma in da za su ga kowace irin aya ce, ba za su yi imani da ita ba. Har ma idan sun zo maka suna jayayya da kai, (sai) waɗanda suka kafirta su riƙa cewa: "Ai wannan ba komai ba ne face tatsuniyoyin mutanen farko."

(26) Kuma suna hana (mutane) sauraren sa (Alkur'ani), kuma su kansu suna ƙara nesanta da shi; kuma ba kowa suke hallakarwa ba face kawunansu, sai dai su ba sa jin hakan

(27) Da kuma za ka ga lokacin da ake tsayar da su a gaban wuta, sai su ce: "Kaiconmu, ina ma da za a mayar da mu (duniya), to da ba za mu sake ƙaryata ayoyin Ubangijinmu ba, kuma za mu zamanto cikin muminai."

بَلْ بَدَا لَهُم مَّا كَانُوا يُخْفُونَ مِن قَبْلُ ۖ وَلَوْ رُدُّوا لَعَادُوا لِمَا نُهُوا عَنْهُ
وَإِنَّهُمْ لَكَاذِبُونَ ﴿٢٨﴾ وَقَالُوا إِنْ هِيَ إِلَّا حَيَاتُنَا الدُّنْيَا وَمَا نَحْنُ
بِمَبْعُوثِينَ ﴿٢٩﴾ وَلَوْ تَرَىٰ إِذْ وُقِفُوا عَلَىٰ رَبِّهِمْ ۚ قَالَ أَلَيْسَ هَٰذَا
بِالْحَقِّ ۚ قَالُوا بَلَىٰ وَرَبِّنَا ۚ قَالَ فَذُوقُوا الْعَذَابَ بِمَا كُنتُمْ تَكْفُرُونَ
﴿٣٠﴾ قَدْ خَسِرَ الَّذِينَ كَذَّبُوا بِلِقَاءِ اللَّهِ ۖ حَتَّىٰ إِذَا جَاءَتْهُمُ السَّاعَةُ
بَغْتَةً قَالُوا يَا حَسْرَتَنَا عَلَىٰ مَا فَرَّطْنَا فِيهَا وَهُمْ يَحْمِلُونَ أَوْزَارَهُمْ
عَلَىٰ ظُهُورِهِمْ ۚ أَلَا سَاءَ مَا يَزِرُونَ ﴿٣١﴾ وَمَا الْحَيَاةُ الدُّنْيَا
إِلَّا لَعِبٌ وَلَهْوٌ ۖ وَلَلدَّارُ الْآخِرَةُ خَيْرٌ لِّلَّذِينَ يَتَّقُونَ ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ
﴿٣٢﴾ قَدْ نَعْلَمُ إِنَّهُ لَيَحْزُنُكَ الَّذِي يَقُولُونَ ۖ فَإِنَّهُمْ لَا يُكَذِّبُونَكَ
وَلَٰكِنَّ الظَّالِمِينَ بِآيَاتِ اللَّهِ يَجْحَدُونَ ﴿٣٣﴾ وَلَقَدْ كُذِّبَتْ
رُسُلٌ مِّن قَبْلِكَ فَصَبَرُوا عَلَىٰ مَا كُذِّبُوا وَأُوذُوا حَتَّىٰ أَتَاهُمْ
نَصْرُنَا ۚ وَلَا مُبَدِّلَ لِكَلِمَاتِ اللَّهِ ۚ وَلَقَدْ جَاءَكَ مِن نَّبَإِي الْمُرْسَلِينَ
﴿٣٤﴾ وَإِن كَانَ كَبُرَ عَلَيْكَ إِعْرَاضُهُمْ فَإِنِ اسْتَطَعْتَ أَن تَبْتَغِيَ
نَفَقًا فِي الْأَرْضِ أَوْ سُلَّمًا فِي السَّمَاءِ فَتَأْتِيَهُم بِآيَةٍ ۚ وَلَوْ شَاءَ
اللَّهُ لَجَمَعَهُمْ عَلَى الْهُدَىٰ ۚ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ الْجَاهِلِينَ ﴿٣٥﴾

(28) A'a, ba haka ba ne, abin da suke ɓoyewa a da shi ne ya bayyana a gare su[1]; kuma in da za a mayar da su, to da sun koma kan abin da aka hana su. Kuma lalle su tabbas maƙaryata ne

(29) Kuma suka ce: "Ba wata (rayuwa) sai rayuwarmu ta duniya, kuma mu ba waɗanda za a sake tashin mu ba ne."

(30) Kuma in da za ka ga lokacin da aka tsayar da su a gaban Ubangjinsu; ya ce: "Shin ashe wannan ba gaskiya ne ba?" Sai su ce: "Gaskiya ne, muna rantsuwa da Ubangijinmu." Sai Ya ce: "To ku ɗanɗani azaba saboda abin da kuka kasance kuna yi na kafirci."

(31) Haƙiƙa waɗanda suka ƙaryata haɗuwa da Allah sun yi hasara; har sai lokacin da alƙiyama ta zo musu ba zato ba tsammani, sai su ce: "Kaiconmu kan irin sakacin da muka yi a cikinta (duniya)," alhalin kuwa suna ɗauke da kayan laifukansu a bayansu. Ku saurara, abin da suka ɗauka na laifi ya munana matuƙa

(32) Kuma rayuwar duniya ba komai ba ce face wasa da sharholiya; kuma lalle gidan lahira shi ne mafi alheri ga waɗanda suke kiyaye dokokin (Allah). Shin ba za ku hankalta ba?

(33) Haƙiƙa Muna da cikakkiyar masaniyar cewa, lalle irin abin da suke faɗa yakan baƙanta maka rai; to a gaskiya su ba kai suke ƙaryatawa ba, sai dai azzalumai suna jayayya ne da ayoyin Allah

(34) Kuma lalle haƙiƙa an ƙaryata waɗansu manzanni a gabaninka, sai suka yi haƙuri a kan ƙaryata su da aka yi, kuma an cutar da su, har sai da taimakonmu ya zo musu. Kuma babu wanda ya isa ya musanya kalmomin Allah. Kuma lalle haƙiƙa wani sashi na labarin manzanni ya zo maka

(35) Kuma idan bijirewarsu ta dame ka, to idan har kana iya haƙa rami a cikin ƙasa, ko kuma (ka samu) wani tsani ka hau sama, don ka zo musu da wata aya, (to ka yi hakan). Kuma in da Allah Ya ga dama, tabbas da Ya tara su gaba ɗaya a kan shiriya. Don haka kada ka kasance cikin jahilai

(1) A duniya suna ɓoye gaskiyar manzancin Annabi ( ) duk da cewa sun san gaskiyarsa.

إِنَّمَا يَسْتَجِيبُ ٱلَّذِينَ يَسْمَعُونَ ۘ وَٱلْمَوْتَىٰ يَبْعَثُهُمُ ٱللَّهُ ثُمَّ إِلَيْهِ
يُرْجَعُونَ ﴿٣٦﴾ وَقَالُوا۟ لَوْلَا نُزِّلَ عَلَيْهِ ءَايَةٌ مِّن رَّبِّهِۦ ۚ قُلْ إِنَّ ٱللَّهَ
قَادِرٌ عَلَىٰٓ أَن يُنَزِّلَ ءَايَةً وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٣٧﴾ وَمَا
مِن دَآبَّةٍ فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا طَٰٓئِرٍ يَطِيرُ بِجَنَاحَيْهِ إِلَّآ أُمَمٌ أَمْثَالُكُم ۚ
مَّا فَرَّطْنَا فِى ٱلْكِتَٰبِ مِن شَىْءٍ ۚ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّهِمْ يُحْشَرُونَ ﴿٣٨﴾
وَٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا صُمٌّ وَبُكْمٌ فِى ٱلظُّلُمَٰتِ ۗ مَن يَشَإِ
ٱللَّهُ يُضْلِلْهُ وَمَن يَشَأْ يَجْعَلْهُ عَلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٣٩﴾ قُلْ
أَرَءَيْتَكُمْ إِنْ أَتَىٰكُمْ عَذَابُ ٱللَّهِ أَوْ أَتَتْكُمُ ٱلسَّاعَةُ أَغَيْرَ ٱللَّهِ
تَدْعُونَ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٤٠﴾ بَلْ إِيَّاهُ تَدْعُونَ فَيَكْشِفُ
مَا تَدْعُونَ إِلَيْهِ إِن شَآءَ وَتَنسَوْنَ مَا تُشْرِكُونَ ﴿٤١﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَآ
إِلَىٰٓ أُمَمٍ مِّن قَبْلِكَ فَأَخَذْنَٰهُم بِٱلْبَأْسَآءِ وَٱلضَّرَّآءِ لَعَلَّهُمْ
يَتَضَرَّعُونَ ﴿٤٢﴾ فَلَوْلَآ إِذْ جَآءَهُم بَأْسُنَا تَضَرَّعُوا۟ وَلَٰكِن قَسَتْ
قُلُوبُهُمْ وَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيْطَٰنُ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٤٣﴾ فَلَمَّا
نَسُوا۟ مَا ذُكِّرُوا۟ بِهِۦ فَتَحْنَا عَلَيْهِمْ أَبْوَٰبَ كُلِّ شَىْءٍ حَتَّىٰٓ
إِذَا فَرِحُوا۟ بِمَآ أُوتُوٓا۟ أَخَذْنَٰهُم بَغْتَةً فَإِذَا هُم مُّبْلِسُونَ ﴿٤٤﴾

(36) Lalle masu ji su ne kawai suke amsa (kiranka). Matattu kuwa Allah zai tashe su (ranar alƙiyama), sannan zuwa gare Shi za a mayar da su

(37) Kuma suka ce: "Ina ma da an saukar masa da wata aya daga Ubangijinsa ?" Ka ce: "Lalle Allah Mai iko ne a kan Ya saukar da kowace irin aya, sai dai yawancinsu ba sa sanin (haka)."

(38) Kuma babu wata dabba da take tafiya a bayan ƙasa, kuma babu wani tsuntsu da yake tashi da fukafukansa, face (su ma) al'ummomi ne irinku. Ba Mu yi sakacin barin wani abu ba a cikin littafi, sannan kuma zuwa ga Ubangijinsu ne za a tara su

(39) Waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu su kurame ne, kuma bebaye ne, suna cikin duffai. Wanda Allah Ya ga dama sai Ya ɓatar da shi, wanda kuwa Ya ga dama sai Ya ɗora shi a kan tafarki madaidaici

(40) Ka ce; "Ku ba ni labari, idan da a ce azabar Allah za ta zo muku ko alƙiyama ta zo muku, shin wanin Allah za ku kira, in har kun kasance masu gaskiya?"

(41) Ba haka ba ne, (Allah) Shi kaɗai za ku kira, sai Ya yaye abin da kuke roƙonsa a kai idan Ya ga dama, kuma za ku manta abin da kuke haɗa Allah da shi wajen bauta

(42) Kuma lalle Mun aika da (manzanni) zuwa ga al'ummomin da suka gabace ka, sai Muka ɗora musu tsananin talauci da cutuka ko sa ƙasƙantar da kai

(43) To me ya hana lokacin da musibarmu ta zo musu, su ƙasƙantar da kai? Sai dai kuma zukatansu ne suka ƙeƙashe, Shaiɗan kuma ya ƙawata musu abin da suka kasance suna aikatawa

(44) To yayin da suka yi watsi da abin da aka yi musu wa'azi da shi, sai Muka buɗe musu ƙofofin kowane irin abu, har zuwa lokacin da suka yi fariya da abin da aka ba su, sai Muka damƙe su ba zato ba tsammani, sai ga su suna masu yanke ƙauna (daga kowane alheri)

فَقُطِعَ دَابِرُ ٱلْقَوْمِ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ ۚ وَٱلْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٤٥﴾
قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِنْ أَخَذَ ٱللَّهُ سَمْعَكُمْ وَأَبْصَٰرَكُمْ وَخَتَمَ عَلَىٰ قُلُوبِكُم
مَّنْ إِلَٰهٌ غَيْرُ ٱللَّهِ يَأْتِيكُم بِهِ ۗ ٱنظُرْ كَيْفَ نُصَرِّفُ ٱلْءَايَٰتِ
ثُمَّ هُمْ يَصْدِفُونَ ﴿٤٦﴾ قُلْ أَرَءَيْتَكُمْ إِنْ أَتَىٰكُمْ عَذَابُ ٱللَّهِ
بَغْتَةً أَوْ جَهْرَةً هَلْ يُهْلَكُ إِلَّا ٱلْقَوْمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٤٧﴾ وَمَا
نُرْسِلُ ٱلْمُرْسَلِينَ إِلَّا مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ ۖ فَمَنْ ءَامَنَ وَأَصْلَحَ
فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٤٨﴾ وَٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا
يَمَسُّهُمُ ٱلْعَذَابُ بِمَا كَانُوا۟ يَفْسُقُونَ ﴿٤٩﴾ قُل لَّآ أَقُولُ لَكُمْ
عِندِى خَزَآئِنُ ٱللَّهِ وَلَآ أَعْلَمُ ٱلْغَيْبَ وَلَآ أَقُولُ لَكُمْ إِنِّى مَلَكٌ ۖ
إِنْ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ إِلَىَّ ۚ قُلْ هَلْ يَسْتَوِى ٱلْأَعْمَىٰ وَٱلْبَصِيرُ ۚ
أَفَلَا تَتَفَكَّرُونَ ﴿٥٠﴾ وَأَنذِرْ بِهِ ٱلَّذِينَ يَخَافُونَ أَن يُحْشَرُوٓا۟ إِلَىٰ
رَبِّهِمْ لَيْسَ لَهُم مِّن دُونِهِۦ وَلِىٌّ وَلَا شَفِيعٌ لَّعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ
﴿٥١﴾ وَلَا تَطْرُدِ ٱلَّذِينَ يَدْعُونَ رَبَّهُم بِٱلْغَدَوٰةِ وَٱلْعَشِىِّ يُرِيدُونَ
وَجْهَهُۥ ۖ مَا عَلَيْكَ مِنْ حِسَابِهِم مِّن شَىْءٍ وَمَا مِنْ حِسَابِكَ
عَلَيْهِم مِّن شَىْءٍ فَتَطْرُدَهُمْ فَتَكُونَ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٥٢﴾

(45) Da haka ne aka tumɓuke tushen waɗanda suka yi zalunci. Kuma yabo da kirari sun tabbata ga Allah Ubangijin talikai

(46) Ka ce: "Ku ba ni labari, yanzu idan Allah zai ɗauke jinku da ganinku, kuma Ya ɗora murfi a zukatanku, wane abin bauta ne wanda ba Allah ba, da zai dawo muku da shi?" Duba ka ga yadda Muke sarrafa ayoyi, amma duk da haka suna bijirewa

(47) Ka ce: "Ku ba ni labari, idan da azabar Allah za ta zo muku ba zato ba tsammani ko kuma cikin sani, to shin za a hallakar da (wasu) ba azzaluman mutane ba?"

(48) Kuma ba ma aiko da manzanni sai suna masu bushara masu gargaɗi; sannan duk wanda ya yi imani kuma ya kyautata aiki, to babu tsoro a tattare da su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba

(49) Waɗanda kuwa suka ƙaryata ayoyinmu, azaba za ta shafe su saboda abin da suka kasance suna yi na fasiƙanci

(50) Ka ce: "Ni ba zan ce da ku a wajena taskokin Allah suke ba, kuma ni ban san gaibu ba, kuma ni ba zan ce da ku ni mala'ika ne ba; ni ba abin da nake bi sai abin da aka yi mini wahayinsa." Ka ce: "Yanzu makaho da mai gani za su yi daidai? To me ya sa ba za ku yi tunani ba?"

(51) Kuma ka yi gargaɗi da shi (Alƙur'ani) ga waɗanda suke jin tsoron a tattara su a gaban Ubangijinsu, ba su da wani majiɓincin lamari in ba Shi ba, kuma ba su da wani mai ceto, don su kiyaye dokokin Allah

(52) Kuma kada ka kori waɗannan da suke bauta wa Ubangijinsu safe da yamma, suna nufin Fuskarsa (watau suna yi don Shi kaɗai); ba wani abu na haƙƙinsu a kanka, kuma babu wani abu na haƙƙinka a kansu, balle ka kore su, sai ka kasance cikin azzalumai.[1]

(1) Daga nan zuwa aya ta 54 suna magana ne game da mushirikan Larabawa da suka nuna wa Manzon Allah ( ) cewa za su musulunta amma da sharaɗin zai kori Musulmi talakawa daga majalisarsa don kada su riƙa yi musu rashin kunya. Sai Allah ( ) ya hana shi aikata hakan.

وَكَذَٰلِكَ فَتَنَّا بَعْضَهُم بِبَعْضٍ لِّيَقُولُوٓا۟ أَهَٰٓؤُلَآءِ مَنَّ ٱللَّهُ
عَلَيْهِم مِّنۢ بَيْنِنَآ ۗ أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِأَعْلَمَ بِٱلشَّٰكِرِينَ ﴿٥٣﴾ وَإِذَا
جَآءَكَ ٱلَّذِينَ يُؤْمِنُونَ بِـَٔايَٰتِنَا فَقُلْ سَلَٰمٌ عَلَيْكُمْ ۖ كَتَبَ
رَبُّكُمْ عَلَىٰ نَفْسِهِ ٱلرَّحْمَةَ ۙ أَنَّهُۥ مَنْ عَمِلَ مِنكُمْ سُوٓءًۢا
بِجَهَٰلَةٍ ثُمَّ تَابَ مِنۢ بَعْدِهِۦ وَأَصْلَحَ فَأَنَّهُۥ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٥٤﴾
وَكَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلْـَٔايَٰتِ وَلِتَسْتَبِينَ سَبِيلُ ٱلْمُجْرِمِينَ
﴿٥٥﴾ قُلْ إِنِّى نُهِيتُ أَنْ أَعْبُدَ ٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ ۚ قُل
لَّآ أَتَّبِعُ أَهْوَآءَكُمْ قَدْ ضَلَلْتُ إِذًا وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُهْتَدِينَ
﴿٥٦﴾ قُلْ إِنِّى عَلَىٰ بَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّى وَكَذَّبْتُم بِهِۦ ۚ مَا عِندِى مَا
تَسْتَعْجِلُونَ بِهِۦٓ ۚ إِنِ ٱلْحُكْمُ إِلَّا لِلَّهِ ۖ يَقُصُّ ٱلْحَقَّ ۖ وَهُوَ
خَيْرُ ٱلْفَٰصِلِينَ ﴿٥٧﴾ قُل لَّوْ أَنَّ عِندِى مَا تَسْتَعْجِلُونَ بِهِۦ لَقُضِىَ
ٱلْأَمْرُ بَيْنِى وَبَيْنَكُمْ ۗ وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٥٨﴾ ۞ وَعِندَهُۥ
مَفَاتِحُ ٱلْغَيْبِ لَا يَعْلَمُهَآ إِلَّا هُوَ ۚ وَيَعْلَمُ مَا فِى ٱلْبَرِّ
وَٱلْبَحْرِ ۚ وَمَا تَسْقُطُ مِن وَرَقَةٍ إِلَّا يَعْلَمُهَا وَلَا حَبَّةٍ فِى ظُلُمَٰتِ
ٱلْأَرْضِ وَلَا رَطْبٍ وَلَا يَابِسٍ إِلَّا فِى كِتَٰبٍ مُّبِينٍ ﴿٥٩﴾

(53) Kuma kamar haka ne Muka jarrabi sashinsu da sashi, domin su ce: "Yanzu waɗannan su ne Allah Ya yi wa baiwa daga cikinmu?" Ashe Allah ba Shi ne Mafi sanin masu godiya (gare Shi) ba?

(54) Kuma idan waɗanda suke yin imani da ayoyinmu sun zo wurinka, to ka ce: "Sallama a gare ku;" Ubangijinku Ya wajabta wa kansa yin rahama cewa, lalle cikinku duk wanda ya aikata wani mummunan aiki bisa ga jahilci, sannan daga baya ya tuba kuma ya kyautata aiki, to Shi Mai gafara ne, Mai jin ƙai."

(55) Kuma kamar haka ne Muke rarrabe ayoyi domin tafarkin masu laifuka ya bayyana

(56) Ka ce: "Lalle ni an hana ni in bauta wa abubuwan da kuke bauta wa ba Allah ba." Ka ce: "Ba zan bi soye-soyen zukatanku ba, (idan har zan bi son zuciyarku), to haƙiƙa na ɓata, kuma da ban zama cikin shiryayyu ba kenan"

(57) Ka ce: "Lalle ni ina kan hujja mai ƙarfi daga Ubangijina, ku kuma kun ƙaryata ta. Abin da kuke so in gaggauto muku da shi, ba a hannuna yake ba. Hukunci yana hannun Allah ne Shi kaɗai; Shi ne Yake bayar da labarin gaskiya, kuma Shi ne Fiyayyen masu rarrabewa (tsakanin ƙarya da gaskiya)"

(58) Ka ce: "Da a ce abin da kuke nema a gaggauto muku da shi a wurina yake, to tabb
ةةةas da ta faru ta ƙare tsakanina da ku. Kuma Allah Shi ne Mafi sanin su wane ne azzalumai

(59) "Kuma mabuɗan gaibu a wurinsa suke Shi kaɗai[1], babu wanda ya san su sai Shi. Kuma Ya san ƙididdigar abin da yake kan tudu da na ruwa. Kuma babu wani ganyen itace da zai faɗo, face sai Ya san da shi, kuma ba wata ƙwaya da take cikin duhun ƙasa, kuma ba wani ɗanyen abu ko busasshe, face (bayaninsa) yana cikin Littafi mabayyani.

(1) Mabuɗan gaibu biyar ne babu wanda ya san su sai Allah. Su ne suka zo a ƙarshen Suratu Luƙman aya ta 34.

وَهُوَ ٱلَّذِى يَتَوَفَّىٰكُم بِٱلَّيْلِ وَيَعْلَمُ مَا جَرَحْتُم بِٱلنَّهَارِ ثُمَّ
يَبْعَثُكُمْ فِيهِ لِيُقْضَىٰٓ أَجَلٌ مُّسَمًّى ۖ ثُمَّ إِلَيْهِ مَرْجِعُكُمْ ثُمَّ
يُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٦٠﴾ وَهُوَ ٱلْقَاهِرُ فَوْقَ عِبَادِهِۦ
وَيُرْسِلُ عَلَيْكُمْ حَفَظَةً حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَ أَحَدَكُمُ ٱلْمَوْتُ تَوَفَّتْهُ
رُسُلُنَا وَهُمْ لَا يُفَرِّطُونَ ﴿٦١﴾ ثُمَّ رُدُّوٓا۟ إِلَى ٱللَّهِ مَوْلَىٰهُمُ ٱلْحَقِّ ۚ
أَلَا لَهُ ٱلْحُكْمُ وَهُوَ أَسْرَعُ ٱلْحَٰسِبِينَ ﴿٦٢﴾ قُلْ مَن يُنَجِّيكُم مِّن
ظُلُمَٰتِ ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ تَدْعُونَهُۥ تَضَرُّعًا وَخُفْيَةً لَّئِنْ أَنجَىٰنَا مِنْ
هَٰذِهِۦ لَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿٦٣﴾ قُلِ ٱللَّهُ يُنَجِّيكُم مِّنْهَا وَمِن كُلِّ كَرْبٍ
ثُمَّ أَنتُمْ تُشْرِكُونَ ﴿٦٤﴾ قُلْ هُوَ ٱلْقَادِرُ عَلَىٰٓ أَن يَبْعَثَ عَلَيْكُمْ عَذَابًا مِّن
فَوْقِكُمْ أَوْ مِن تَحْتِ أَرْجُلِكُمْ أَوْ يَلْبِسَكُمْ شِيَعًا وَيُذِيقَ بَعْضَكُم
بَأْسَ بَعْضٍ ۗ ٱنظُرْ كَيْفَ نُصَرِّفُ ٱلْءَايَٰتِ لَعَلَّهُمْ يَفْقَهُونَ ﴿٦٥﴾ وَكَذَّبَ
بِهِۦ قَوْمُكَ وَهُوَ ٱلْحَقُّ ۚ قُل لَّسْتُ عَلَيْكُم بِوَكِيلٍ ﴿٦٦﴾ لِّكُلِّ نَبَإٍ
مُّسْتَقَرٌّ ۚ وَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿٦٧﴾ وَإِذَا رَأَيْتَ ٱلَّذِينَ يَخُوضُونَ فِىٓ ءَايَٰتِنَا
فَأَعْرِضْ عَنْهُمْ حَتَّىٰ يَخُوضُوا۟ فِى حَدِيثٍ غَيْرِهِۦ ۚ وَإِمَّا يُنسِيَنَّكَ
ٱلشَّيْطَٰنُ فَلَا تَقْعُدْ بَعْدَ ٱلذِّكْرَىٰ مَعَ ٱلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٦٨﴾

(60) "Kuma Shi ne Yake karɓar rayukanku da daddare[1], kuma Ya san abin da kuka aikata da rana, sannan Ya tayar da ku a cikinta (ranar), har zuwa lokacin da zai zartar da wani ajali sananne, sannan zuwa gare Shi ne makomarku take, sannan zai ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa

(61) "Kuma Shi ne wanda Yake da iko a kan bayinsa, kuma Yana aiko muku masu tsaro, har zuwa lokacin da mutuwa za ta zo wa ɗayanku, sai manzanninmu su karɓi ransa, kuma su ba sa yin sakaci

(62) "Sannan sai a mayar da su zuwa ga Allah Majiɓincin lamarinsu na gaskiya. Ku saurara, dukkan hukunci nasa ne, kuma Shi ne Mafi gaggawar masu hisabi."

(63) Ka ce: "Wane ne yake tserar da ku daga cikin duffai na tudu da na kogi, kuna roƙon sa a fili da a ɓoye (cewa): "Tabbas, in da zai tserar da mu daga wannan, to lalle za mu kasance cikin masu godiya."

(64) Ka ce: "Allah ne zai tserar da ku daga cikinsa (tsoron), da ma duk wani baƙin ciki, sannan sai ga ku kuna yin shirka."

(65) Ka ce: "Shi ne Mai cikakken ikon Ya aiko muku da azaba ta samanku ko ta ƙarƙashin ƙafafuwanku ko Ya mayar da ku ƙungiyoyi daban-daban, kuma Ya ɗanɗana wa sashinku azabar sashi." Duba ka ga yadda Muke bayyana ayoyi, don su fahimta

(66) Kuma mutanenka sun ƙaryata shi (Alƙur'ani) alhali shi ne gaskiya. Ka ce: "Ni ba wakili ne a kanku ba

(67) "Kowane labari yana da lokaci ne na musamman. Kuma da sannu za ku sani."


(68) Kuma idan ka ga waɗanda suke kutsawa cikin ayoyinmu (suna izgili), to ka rabu da su, har sai sun canja wani zancen da ba wancan ba. Amma in da Shaiɗan zai mantar da kai kuwa, to bayan ka tuna kar ka sake zama tare da azzalumai

(1) Watau lokacin barcinku; ya riƙe ran da ya hukunta masa mutuwa, ya sako wanda lokacin mutuwarsa bai zo ba. duba Suratuz Zumar aya ta 42.

وَمَا عَلَى ٱلَّذِينَ يَتَّقُونَ مِنْ حِسَابِهِم مِّن شَىْءٍ وَلَٰكِن
ذِكْرَىٰ لَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ ﴿٦٩﴾ وَذَرِ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُوا۟ دِينَهُمْ
لَعِبًا وَلَهْوًا وَغَرَّتْهُمُ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا ۚ وَذَكِّرْ بِهِۦٓ أَن
تُبْسَلَ نَفْسٌۢ بِمَا كَسَبَتْ لَيْسَ لَهَا مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلِىٌّ
وَلَا شَفِيعٌ وَإِن تَعْدِلْ كُلَّ عَدْلٍ لَّا يُؤْخَذْ مِنْهَآ ۗ أُو۟لَٰٓئِكَ
ٱلَّذِينَ أُبْسِلُوا۟ بِمَا كَسَبُوا۟ ۖ لَهُمْ شَرَابٌ مِّنْ حَمِيمٍ
وَعَذَابٌ أَلِيمٌۢ بِمَا كَانُوا۟ يَكْفُرُونَ ﴿٧٠﴾ قُلْ أَنَدْعُوا۟ مِن دُونِ
ٱللَّهِ مَا لَا يَنفَعُنَا وَلَا يَضُرُّنَا وَنُرَدُّ عَلَىٰٓ أَعْقَٰبِنَا بَعْدَ إِذْ
هَدَىٰنَا ٱللَّهُ كَٱلَّذِى ٱسْتَهْوَتْهُ ٱلشَّيَٰطِينُ فِى ٱلْأَرْضِ
حَيْرَانَ لَهُۥٓ أَصْحَٰبٌ يَدْعُونَهُۥٓ إِلَى ٱلْهُدَى ٱئْتِنَا ۗ قُلْ إِنَّ
هُدَى ٱللَّهِ هُوَ ٱلْهُدَىٰ ۖ وَأُمِرْنَا لِنُسْلِمَ لِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٧١﴾ وَأَنْ
أَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَٱتَّقُوهُ ۚ وَهُوَ ٱلَّذِىٓ إِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ﴿٧٢﴾ وَهُوَ
ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ بِٱلْحَقِّ ۖ وَيَوْمَ يَقُولُ كُن
فَيَكُونُ ۚ قَوْلُهُ ٱلْحَقُّ ۚ وَلَهُ ٱلْمُلْكُ يَوْمَ يُنفَخُ فِى ٱلصُّورِ ۚ
عَٰلِمُ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ ۚ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْخَبِيرُ ﴿٧٣﴾

(69) Kuma babu wani laifi a kan waɗanda suke tsoron haɗuwarsu da Allah (don sun zauna da su), sai dai kuma (dole su yi) musu wa'azi don su tsorata
(70) Ka rabu da waɗanda suka ɗauki addininsu wasa da sharholiya, rayuwarsu ta duniya kuma ta ruɗe su. Ka kuma yi gargaɗi da shi (Alƙur'ani), saboda kada a jarrabi rai da abin da ya aikata wanda ba ya da wani mataimaki ko mai ceto ban da Allah, ko da kuwa (ran) ya ba da kowace irin fansa ba za a karɓa ba daga gare shi. Waɗancan su ne waɗanda aka kange (don yi musu azaba) saboda abin da suka aikata; suna da abin sha na tafasasshen ruwa da kuma azaba mai raɗaɗi saboda abin da suka zamanto suna kafircewa (da shi)
(71) Ka ce: "Shin yanzu ma riƙa bauta wa wani wanda ba Allah ba, abin da ba zai amfane mu ba, kuma ba zai cutar da mu ba, mu koma gidan jiya (kafirai) bayan kuwa Allah Ya shiryar da mu, (mu koma) kamar wanda shaiɗanu suka ɓatar da shi yana ta ɗimuwa a bayan ƙasa, ga shi da wasu abokai suna kiran sa zuwa ga shiriya, (suna cewa): "Ka zo (mu bi tafarkin shiriya)[1]." Ka ce: "Lalle shiriyar Allah fa ita kaɗai ce shiriya; kuma mu an umarce mu da mu miƙa wuya ne kaɗai ga Ubangijin talikai
(72) "Kuma ku tsayar da salla kuma ku kiyaye dokokinsa. Kuma Shi ne Wanda za a tara ku zuwa gare Shi
(73) Y"Kuma Shi ne Wanda ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya; kuma (ku tuna) ranar da zai ce da abu: 'Kasance!' Nan take sai ya kasance. Maganarsa gaskiya ce. Kuma Shi ne Yake da cikakken mulki a ranar da za a busa ƙaho Masanin gaibu da sarari, kuma Shi ne Mai hikima, Mai cikakken sani."

(1) Misali ne na wanda ya saki Musulunci ya kama shirka ko ɓata, ya zama kamar mutumin da aljanu suka ɗauke shi suka tafi da shi suka jefar da shi a ƙurgurmin daji. Don haka ya yi nisan da ba zai ji kira ba, balle ya gane hanyar dawowa.


* وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ لِأَبِيهِ ءَازَرَ أَتَتَّخِذُ أَصْنَامًا ءَالِهَةً إِنِّيٓ
أَرَىٰكَ وَقَوْمَكَ فِي ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٧٤﴾ وَكَذَٰلِكَ نُرِيٓ إِبْرَٰهِيمَ
مَلَكُوتَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَلِيَكُونَ مِنَ ٱلْمُوقِنِينَ
﴿٧٥﴾ فَلَمَّا جَنَّ عَلَيْهِ ٱلَّيْلُ رَءَا كَوْكَبًا ۖ قَالَ هَٰذَا رَبِّي ۖ فَلَمَّآ أَفَلَ
قَالَ لَآ أُحِبُّ ٱلْأَٰفِلِينَ ﴿٧٦﴾ فَلَمَّا رَءَا ٱلْقَمَرَ بَازِغًا قَالَ هَٰذَا
رَبِّي ۖ فَلَمَّآ أَفَلَ قَالَ لَئِن لَّمْ يَهْدِنِي رَبِّي لَأَكُونَنَّ مِنَ ٱلْقَوْمِ
ٱلضَّآلِّينَ ﴿٧٧﴾ فَلَمَّا رَءَا ٱلشَّمْسَ بَازِغَةً قَالَ هَٰذَا رَبِّي هَٰذَآ
أَكْبَرُ ۖ فَلَمَّآ أَفَلَتْ قَالَ يَٰقَوْمِ إِنِّي بَرِيٓءٌ مِّمَّا تُشْرِكُونَ
﴿٧٨﴾ إِنِّي وَجَّهْتُ وَجْهِيَ لِلَّذِي فَطَرَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ
حَنِيفًا ۖ وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٧٩﴾ وَحَآجَّهُۥ قَوْمُهُۥ ۚ قَالَ
أَتُحَٰٓجُّوٓنِّي فِي ٱللَّهِ وَقَدْ هَدَىٰنِ ۚ وَلَآ أَخَافُ مَا تُشْرِكُونَ بِهِۦٓ
إِلَّآ أَن يَشَآءَ رَبِّي شَيْـًٔا ۗ وَسِعَ رَبِّي كُلَّ شَيْءٍ عِلْمًا ۗ أَفَلَا
تَتَذَكَّرُونَ ﴿٨٠﴾ وَكَيْفَ أَخَافُ مَآ أَشْرَكْتُمْ وَلَا تَخَافُونَ
أَنَّكُمْ أَشْرَكْتُم بِٱللَّهِ مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِۦ عَلَيْكُمْ سُلْطَٰنًا ۚ
فَأَىُّ ٱلْفَرِيقَيْنِ أَحَقُّ بِٱلْأَمْنِ ۖ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٨١﴾

(74) Kuma (ka tuna) lokacin da Ibrahimu ya ce da babansa Azaru: "Yanzu ka riƙi gumaka a matsayin alloli? Lalle ni ina ganin ka kai da mutanenka, kuna cikin ƃata mabayyani."
(75)Kuma kamar haka ne Muke nuna wa Ibrahimu halittun sammai da ƙasa, domin ya kasance cikin masu sakankancewa
(76) To yayin da dare ya lulluƃe shi, ya ga tauraro, sai ya ce; "Wannan shi ne ubangijina;"(1) sannan yayin da ya ƃace, sai ya ce: "Ni fa ba na son abubuwa masu gushewa."
(77) Sa'annan yayin da ya ga wata ya fito, sai ya ce; "Wannan shi ne ubangijina;" sannan yayin da ya gushe, sai ya ce: "Lalle idan Ubangijina bai shiryar da ni ba, haƙiƙa zan kasance daga cikin mutane ƃatattu."
(78) Sannan yayin da ya ga rana ta hudo, sai ya ce: "Wannan shi ne ubangijina, wannan shi ya fi girma;" sannan yayin da ta ƃace, sai ya ce: "Ya ku mutanena, haƙiƙa ni ba ruwana da abin da kuke haɗa Allah da shi
(79) "Lalle ni kam na juyar da fuskata ga Wanda Ya halicci sammai da ƙasa, ina mai kauce wa ƃarna kuma ni ba na cikin masu yin shirka."
(80) PKuma mutanensa sun yi jayayya da shi; (sai) ya ce: "Shin yanzu kwa riƙa jayayya da ni game da (kaɗaitakar) Allah, alhalin kuwa Ya shiryar da ni? Kuma ba na jin tsoron abin da kuke sanya wa Allah kishiya da shi, sai abin da Ubangijina Ya ga dama. Kuma ilimin Ubangijina ya yalwaci komai. Shin ba za ku wa'azantu ba?
(81) "To ta ƙaƙa kuwa zan ji tsoron abin da kuka tara da (Allah), alhali ku kuma ba kwa jin tsoron kun sanya wa Allah kishiya, abin da kuwa bai saukar muku da wata hujja a kai ba? To wane ƃangare ne cikin ƃangarori biyu, ya fi dacewa da samun aminci; in har kun kasance kun sani?

(1) Daga wannan ayar zuwa aya ta 79 Allah ( ) ya koya wa Annabi Ibrahim ( ) hanyar da zai yi wa mutanensa wa'azi cikin hikima da laluma don jan hankalinsu su fahimci abubuwan da suke bauta wa ba ababen bauta ne na gaskiya ba.

ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَمۡ يَلۡبِسُوٓاْ إِيمَٰنَهُم بِظُلۡمٍ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلۡأَمۡنُ
وَهُم مُّهۡتَدُونَ ﴿٨٢﴾ وَتِلۡكَ حُجَّتُنَآ ءَاتَيۡنَٰهَآ إِبۡرَٰهِيمَ عَلَىٰ
قَوۡمِهِۦۚ نَرۡفَعُ دَرَجَٰتٖ مَّن نَّشَآءُۗ إِنَّ رَبَّكَ حَكِيمٌ عَلِيمٞ ﴿٨٣﴾
وَوَهَبۡنَا لَهُۥٓ إِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَۚ كُلّٗا هَدَيۡنَاۚ وَنُوحٗا هَدَيۡنَا
مِن قَبۡلُۖ وَمِن ذُرِّيَّتِهِۦ دَاوُۥدَ وَسُلَيۡمَٰنَ وَأَيُّوبَ وَيُوسُفَ
وَمُوسَىٰ وَهَٰرُونَۚ وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ﴿٨٤﴾
وَزَكَرِيَّا وَيَحۡيَىٰ وَعِيسَىٰ وَإِلۡيَاسَۖ كُلّٞ مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ
﴿٨٥﴾ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَٱلۡيَسَعَ وَيُونُسَ وَلُوطٗاۚ وَكُلّٗا فَضَّلۡنَا عَلَى
ٱلۡعَٰلَمِينَ ﴿٨٦﴾ وَمِنۡ ءَابَآئِهِمۡ وَذُرِّيَّٰتِهِمۡ وَإِخۡوَٰنِهِمۡۖ وَٱجۡتَبَيۡنَٰهُمۡ
وَهَدَيۡنَٰهُمۡ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ﴿٨٧﴾ ذَٰلِكَ هُدَى ٱللَّهِ يَهۡدِي
بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦۚ وَلَوۡ أَشۡرَكُواْ لَحَبِطَ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ
يَعۡمَلُونَ ﴿٨٨﴾ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحُكۡمَ
وَٱلنُّبُوَّةَۚ فَإِن يَكۡفُرۡ بِهَا هَٰٓؤُلَآءِ فَقَدۡ وَكَّلۡنَا بِهَا قَوۡمٗا لَّيۡسُواْ
بِهَا بِكَٰفِرِينَ ﴿٨٩﴾ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ هَدَى ٱللَّهُۖ فَبِهُدَىٰهُمُ ٱقۡتَدِهۡۗ
قُل لَّآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ أَجۡرًاۖ إِنۡ هُوَ إِلَّا ذِكۡرَىٰ لِلۡعَٰلَمِينَ ﴿٩٠﴾

(82) "Waɗanda suka yi imani, kuma ba su garwaya imaninsu da zalunci ba, waɗannan su suke da aminci, kuma su ne shiryayyu."

(83) Kuma waɗancan su ne hujjojinmu da Muka ba wa Ibrahimu su a kan mutanensa. Muna ɗaukaka darajojin waɗanda Muka ga dama. Lalle Ubangijinka Mai hikima ne, Mai yawan sani

(84) Kuma Muka ba shi Ishaƙa da Ya'aƙubu. Kowanne daga cikinsu Mun shiryar da shi, kuma Mun shiryar da Nuhu tun gabaninsu. Kuma daga cikin zurriyarsa akwai Dawudu da Sulaimanu da Ayyuba da Yusufu da Musa da Haruna. Kuma kamar haka ne Muke saka wa masu kyautata (ayyukansu)

(85) Da Zakariyya da Yahaya da Isa da Iliyasu; kowanne daga cikinsu yana cikin salihan bayi

(86) Da Isma'ilu da Alyasa'u da Yunusu da Luɗu. Kowanne daga cikinsu kuma Mun fifita shi a kan (sauran) talikai

(87) Kuma daga cikin iyayensu da zurriyarsu da 'yan'uwansu; duka Mun zaɓe su, kuma Mun shiryar da su zuwa ga tafarki madaidaici

(88) Wannan ita ce shiriyar Allah wadda da ita ne Yake shiryar da wanda Ya ga dama cikin bayinsa. Kuma da a ce sun yi shirka, to lalle da duk abin da suka kasance suna aikatawa ya rushe

(89) Waɗannan su ne waɗanda Muka bai wa littattafai da hukunci da annabta. To idan waɗancan (mutanen Makka) suka kafirce mata (shiriya), to haƙiƙa Mun shirya musu waɗansu mutane waɗanda ba za su kafirce mata ba

(90) Waɗannan su ne waɗanda Allah Ya shiryar; don haka ka yi koyi da irin shiriyarsu. Ka ce: "Ba na roƙon ku wani lada game da shi (Alƙur'ani); shi ba komai ba ne face tunatarwa ga talikai."

وَمَا قَدَرُوا۟ ٱللَّهَ حَقَّ قَدْرِهِۦٓ إِذْ قَالُوا۟ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ عَلَىٰ بَشَرٍ مِّن شَىْءٍ ۗ
قُلْ مَنْ أَنزَلَ ٱلْكِتَٰبَ ٱلَّذِى جَآءَ بِهِۦ مُوسَىٰ نُورًا وَهُدًى
لِّلنَّاسِ ۖ تَجْعَلُونَهُۥ قَرَاطِيسَ تُبْدُونَهَا وَتُخْفُونَ كَثِيرًا ۖ وَعُلِّمْتُم
مَّا لَمْ تَعْلَمُوٓا۟ أَنتُمْ وَلَآ ءَابَآؤُكُمْ ۖ قُلِ ٱللَّهُ ۖ ثُمَّ ذَرْهُمْ فِى خَوْضِهِمْ
يَلْعَبُونَ ﴿٩١﴾ وَهَٰذَا كِتَٰبٌ أَنزَلْنَٰهُ مُبَارَكٌ مُّصَدِّقُ ٱلَّذِى بَيْنَ
يَدَيْهِ وَلِتُنذِرَ أُمَّ ٱلْقُرَىٰ وَمَنْ حَوْلَهَا ۚ وَٱلَّذِينَ يُؤْمِنُونَ بِٱلْءَاخِرَةِ
يُؤْمِنُونَ بِهِۦ ۖ وَهُمْ عَلَىٰ صَلَاتِهِمْ يُحَافِظُونَ ﴿٩٢﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ
ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوْ قَالَ أُوحِىَ إِلَىَّ وَلَمْ يُوحَ إِلَيْهِ شَىْءٌ
وَمَن قَالَ سَأُنزِلُ مِثْلَ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ ۗ وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِى
غَمَرَٰتِ ٱلْمَوْتِ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ بَاسِطُوٓا۟ أَيْدِيهِمْ أَخْرِجُوٓا۟ أَنفُسَكُمُ ۖ
ٱلْيَوْمَ تُجْزَوْنَ عَذَابَ ٱلْهُونِ بِمَا كُنتُمْ تَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ غَيْرَ
ٱلْحَقِّ وَكُنتُمْ عَنْ ءَايَٰتِهِۦ تَسْتَكْبِرُونَ ﴿٩٣﴾ وَلَقَدْ جِئْتُمُونَا
فُرَٰدَىٰ كَمَا خَلَقْنَٰكُمْ أَوَّلَ مَرَّةٍ وَتَرَكْتُم مَّا خَوَّلْنَٰكُمْ وَرَآءَ
ظُهُورِكُمْ ۖ وَمَا نَرَىٰ مَعَكُمْ شُفَعَآءَكُمُ ٱلَّذِينَ زَعَمْتُمْ أَنَّهُمْ فِيكُمْ
شُرَكَٰٓؤُا۟ ۚ لَقَد تَّقَطَّع بَيْنَكُمْ وَضَلَّ عَنكُم مَّا كُنتُمْ تَزْعُمُونَ ﴿٩٤﴾

(91) Kuma ba su girmama Allah haƙiƙanin girman da ya kamace shi ba, yayin da suka ce: "Allah bai saukar wa wani mutum da komai ba." Ka ce: "Wane ne ya saukar da littafin da Musa ya zo da shi, mai haske, kuma mai shiryar da mutane; kuka rika mayar da takardunsa falle-falle, kuna bayyana (wadanda kuke so), kuma kuna ɓoye wani kaso mai yawa; kuma aka sanar da ku abin da ba ku sani ba, ku da ma iyayenku?" Ka ce: "Allah ne (Ya saukar da shi)" Sannan sai ka ƙyale su su yi ta kutsawa cikin ɓarnarsu, suna wasa

(92) Kuma wannan (Alƙur'ani) littafi ne mai albarka, wanda Muka saukar da shi mai gaskata abin da ya gabace shi (na littattafai), kuma don ka gargaɗi uwar alƙaryu (mutanen Makka) da wadanda suke kewaye da ita. Wadanda kuwa suke yin imani da ranar lahira, suna yin imani da shi ne (Alƙur'ani), kuma su suna kiyaye sallolinsu

(93) Kuma wane ne ya fi zalunci kamar wanda ya ƙagi ƙarya ya jingina wa Allah, ko kuma ya ce: "An yiwo mini wahayi," alhalin kuma ba a yi masa wahayin komai ba, da kuma wanda ya ce: "Zan saukar da irin abin da Allah Ya saukar?" Kuma da za ka ga lokacin da kafirai suke cikin magagin mutuwa, mala'iku kuma suna miƙa hannayensu suna cewa: "Ku fito da rayukanku (da kanku), a yau ne za a saka muku da azabar wulaƙanci, saboda irin abin da kuke faɗa game da Allah wanda ba gaskiya ba, kuma kun kasance kuna girman kai game da ayoyinsa."

(94) Kuma lalle haƙiƙa kun zo Mana ɗaiɗai kamar yadda Muka halicce ku a karon fari, kuma kun baro abin da Muka ba ku a bayanku (a duniya), kuma har yanzu ba Ma ganin masu ceton ku waɗanda kuka riya cewa su ne abokanan tarayyarku. Lalle haƙiƙa dangantakar da take tsakaninku ta yanke, kuma abin da kuke riyawa ya ɓace muku

إِنَّ ٱللَّهَ فَالِقُ ٱلْحَبِّ وَٱلنَّوَىٰ ۖ يُخْرِجُ ٱلْحَىَّ مِنَ ٱلْمَيِّتِ وَمُخْرِجُ
ٱلْمَيِّتِ مِنَ ٱلْحَىِّ ۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ ۖ فَأَنَّىٰ تُؤْفَكُونَ ﴿٩٥﴾ فَالِقُ ٱلْإِصْبَاحِ
وَجَعَلَ ٱلَّيْلَ سَكَنًا وَٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ حُسْبَانًا ۚ ذَٰلِكَ تَقْدِيرُ
ٱلْعَزِيزِ ٱلْعَلِيمِ ﴿٩٦﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلنُّجُومَ لِتَهْتَدُوا۟
بِهَا فِى ظُلُمَٰتِ ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ ۗ قَدْ فَصَّلْنَا ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يَعْلَمُونَ
﴿٩٧﴾ وَهُوَ ٱلَّذِىٓ أَنشَأَكُم مِّن نَّفْسٍ وَٰحِدَةٍ فَمُسْتَقَرٌّ وَمُسْتَوْدَعٌ ۗ
قَدْ فَصَّلْنَا ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يَفْقَهُونَ ﴿٩٨﴾ وَهُوَ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ مِنَ
ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجْنَا بِهِۦ نَبَاتَ كُلِّ شَىْءٍ فَأَخْرَجْنَا مِنْهُ
خَضِرًا نُّخْرِجُ مِنْهُ حَبًّا مُّتَرَاكِبًا وَمِنَ ٱلنَّخْلِ مِن طَلْعِهَا قِنْوَانٌ
دَانِيَةٌ وَجَنَّٰتٍ مِّنْ أَعْنَابٍ وَٱلزَّيْتُونَ وَٱلرُّمَّانَ مُشْتَبِهًا وَغَيْرَ
مُتَشَٰبِهٍ ۗ ٱنظُرُوٓا۟ إِلَىٰ ثَمَرِهِۦٓ إِذَآ أَثْمَرَ وَيَنْعِهِۦٓ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكُمْ
لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٩٩﴾ وَجَعَلُوا۟ لِلَّهِ شُرَكَآءَ ٱلْجِنَّ وَخَلَقَهُمْ ۖ
وَخَرَقُوا۟ لَهُۥ بَنِينَ وَبَنَٰتٍۭ بِغَيْرِ عِلْمٍ ۚ سُبْحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يَصِفُونَ
﴿١٠٠﴾ بَدِيعُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ أَنَّىٰ يَكُونُ لَهُۥ وَلَدٌ وَلَمْ تَكُن لَّهُۥ
صَٰحِبَةٌ ۖ وَخَلَقَ كُلَّ شَىْءٍ ۖ وَهُوَ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿١٠١﴾



(95) Lalle Allah ne Yake tsaga ƙwaya da ƙwallon dabino (lokacin tsirowarsa) shi Yake fitar da rayayye daga matacce, kuma Mai fitar da matacce daga rayayye. Mai yin wannan aiki Shi ne Allah; to ta yaya ake kautar da ku?

(96) (Shi ne) Mai keto da hasken safiya, kuma Ya sanya dare don nutsuwa; rana da wata kuma don ƙidayar lokatai. Wannan shiri ne na (Allah) Mabuwayi, Mai yawan sani

(97) Kuma Shi ne Wanda Ya sanya muku taurari domin ku gane hanya da su a cikin duffan tudu da na ruwa. Haƙiƙa Mun bayyana ayoyi ga mutanen da suke da sani

(98) Kuma Shi ne Wanda Ya halicce ku daga rai ɗaya, sannan Ya ajiye ku a wani wurin zama (tsatson namiji) da kuma wani wurin ajiya, (mahaifiyar mace). Haƙiƙa Mun bayyana ayoyi ga mutanen da suke fahimta

(99) Kuma Shi ne Wanda Ya saukar da ruwa daga sama, sai Muka fitar da kowane irin dangin tsiro da shi, sannan Muka fitar da shi (tsiron) (wasu) koraye, daga gare shi kuma Muke fitar da ƙwayoyi a cunkushe daga gare shi. Kuma daga hudar dabino (ake samun) nonuna waɗanda suke dab da ƙasa; da kuma waɗansu lambuna na inabi da zaitun da ruman, masu kama da juna da kuma mabambanta. Ku kalli 'ya'yansu idan suka yi 'ya'ya da kuma lokacin da suka nuna. Lalle game da wannan akwai ayoyi ga mutanen da suka yi imani

(100) Kuma sun sanya wa Allah aljannu a matsayin abokanan tarayya, alhali kuwa Shi ya halicce su; kuma suka ƙago masa 'ya'ya maza da mata, ba tare da wani ilimi ba. Tsarki ya tabbata a gare Shi, kuma Ya ɗaukaka daga irin abin da suke siffanta (Shi da shi)

(101) (Shi ne) Mahagin sammai da ƙasa; ta yaya zai zama Yana da ɗa, ga Shi kuma ba Shi da mata? Kuma Shi ne Ya halicci komai, kuma Shi Masanin komai ne

ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ ۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ خَٰلِقُ كُلِّ شَىْءٍ فَٱعْبُدُوهُ ۚ
وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ وَكِيلٌ ﴿١٠٢﴾ لَّا تُدْرِكُهُ ٱلْأَبْصَٰرُ وَهُوَ
يُدْرِكُ ٱلْأَبْصَٰرَ ۖ وَهُوَ ٱللَّطِيفُ ٱلْخَبِيرُ ﴿١٠٣﴾ قَدْ جَآءَكُم
بَصَآئِرُ مِن رَّبِّكُمْ ۖ فَمَنْ أَبْصَرَ فَلِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَنْ عَمِىَ فَعَلَيْهَا ۚ
وَمَآ أَنَا۠ عَلَيْكُم بِحَفِيظٍ ﴿١٠٤﴾ وَكَذَٰلِكَ نُصَرِّفُ ٱلْءَايَٰتِ
وَلِيَقُولُوا۟ دَرَسْتَ وَلِنُبَيِّنَهُۥ لِقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ﴿١٠٥﴾ ٱتَّبِعْ
مَآ أُوحِىَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ ۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ وَأَعْرِضْ عَنِ ٱلْمُشْرِكِينَ
﴿١٠٦﴾ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَآ أَشْرَكُوا۟ ۗ وَمَا جَعَلْنَٰكَ عَلَيْهِمْ حَفِيظًا ۖ
وَمَآ أَنتَ عَلَيْهِم بِوَكِيلٍ ﴿١٠٧﴾ وَلَا تَسُبُّوا۟ ٱلَّذِينَ يَدْعُونَ
مِن دُونِ ٱللَّهِ فَيَسُبُّوا۟ ٱللَّهَ عَدْوًۢا بِغَيْرِ عِلْمٍ ۗ كَذَٰلِكَ زَيَّنَّا لِكُلِّ أُمَّةٍ
عَمَلَهُمْ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّهِم مَّرْجِعُهُمْ فَيُنَبِّئُهُم بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ
﴿١٠٨﴾ وَأَقْسَمُوا۟ بِٱللَّهِ جَهْدَ أَيْمَٰنِهِمْ لَئِن جَآءَتْهُمْ ءَايَةٌ لَّيُؤْمِنُنَّ
بِهَا ۚ قُلْ إِنَّمَا ٱلْءَايَٰتُ عِندَ ٱللَّهِ ۖ وَمَا يُشْعِرُكُمْ أَنَّهَآ إِذَا جَآءَتْ
لَا يُؤْمِنُونَ ﴿١٠٩﴾ وَنُقَلِّبُ أَفْـِٔدَتَهُمْ وَأَبْصَٰرَهُمْ كَمَا لَمْ
يُؤْمِنُوا۟ بِهِۦٓ أَوَّلَ مَرَّةٍ وَنَذَرُهُمْ فِى طُغْيَٰنِهِمْ يَعْمَهُونَ ﴿١١٠﴾

(102) Wannan Shi ne Allah Ubangijinku; ba wani abin bautawa da gaskiya sai Shi; Mahaliccin komai, don haka ku bauta masa. Kuma Shi Mai kiyayewa ne da komai

(103) Gannai ba sa riskar Sa[1], Shi ne Yake riskar gannai, kuma Shi Mai tausasawa ne, Mai cikakken sani

(104) Hakika hujjoji sun zo muku daga Ubangijinku; don haka duk wanda ya gan su (ya bi su), to ya yi don amfanin kansa ne; duk kuwa wanda ya makance, to kansa ya cuta. Kuma ni ba mai tsaron ku ba ne

(105) Kuma kamar haka ne Muke bayyana ayoyi, don (kafirai) su ce: "Ka koya ne (daga wasu littattafai)", kuma don Mu bayyana shi (Alkur'ani) ga mutanen da suke ganewa

(106) Ka bi abin da aka yi maka wahayi daga Ubangijinka; ba abin bautawa da gaskiya sai Shi; kuma ka kawar da kai daga mushrikai

(107) Kuma da Allah Ya ga dama, da ba su yi shirka ba. Ba Mu kuma sanya ka mai tsaro a kansu ba; kuma kai ba wakili ne a gare su ba

(108) Kuma kada ku zagi waɗanda suke bauta wa ba Allah ba, sai su zagi Allah saboda zalunci, ba tare da sanin (girmansa) ba. Kamar haka ne Muka ƙawata wa kowace al'umma ayyukansu (nagari da munana), sannan zuwa ga Ubangijinsu ne makomarsu take, sai Ya ba su labarin abin da suka kasance suna aikatawa

(109) Kuma sun rantse da Allah iyakar gaskiyarsu cewa, lalle idan har aya ta zo musu, tabbas za su yi imani da ita. Ka ce: "Ai ayoyi daga wajen Allah suke." Kuma wa ya sanar da ku cewa, idan (ayoyin) sun zo ba za su yi imani ba?

(110) Kuma za Mu rika jujjuya zukatansu da gannansu, (daga fahimta da ganin gaskiya) kamar yadda ba su yi imani da shi ba da farko, Mu kuma bar su cikin shisshiginsu suna ɗimuwa

(1) A duniya babu wanda zai ga Allah ƙuru-ƙuru da idonsa. Amma a lahira muminai za su gan shi kamar yadda ya zo a Suratul Kiyama aya ta 22 zuwa 23. Hadisai masu yawa sun tabbatar da hakan.



* وَلَوْ أَنَّنَا نَزَّلْنَآ إِلَيْهِمُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةَ وَكَلَّمَهُمُ ٱلْمَوْتَىٰ وَحَشَرْنَا
عَلَيْهِمْ كُلَّ شَىْءٍ قُبُلًا مَّا كَانُوا۟ لِيُؤْمِنُوٓا۟ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ
وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ يَجْهَلُونَ ﴿١١١﴾ وَكَذَٰلِكَ جَعَلْنَا لِكُلِّ نَبِىٍّ
عَدُوًّا شَيَٰطِينَ ٱلْإِنسِ وَٱلْجِنِّ يُوحِى بَعْضُهُمْ إِلَىٰ بَعْضٍ
زُخْرُفَ ٱلْقَوْلِ غُرُورًا ۚ وَلَوْ شَآءَ رَبُّكَ مَا فَعَلُوهُ ۖ فَذَرْهُمْ وَمَا
يَفْتَرُونَ ﴿١١٢﴾ وَلِتَصْغَىٰٓ إِلَيْهِ أَفْـِٔدَةُ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِٱلْـَٔاخِرَةِ
وَلِيَرْضَوْهُ وَلِيَقْتَرِفُوا۟ مَا هُم مُّقْتَرِفُونَ ﴿١١٣﴾ أَفَغَيْرَ ٱللَّهِ أَبْتَغِى
حَكَمًا وَهُوَ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ إِلَيْكُمُ ٱلْكِتَٰبَ مُفَصَّلًا ۚ
وَٱلَّذِينَ ءَاتَيْنَٰهُمُ ٱلْكِتَٰبَ يَعْلَمُونَ أَنَّهُۥ مُنَزَّلٌ مِّن رَّبِّكَ
بِٱلْحَقِّ ۖ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُمْتَرِينَ ﴿١١٤﴾ وَتَمَّتْ كَلِمَتُ رَبِّكَ
صِدْقًا وَعَدْلًا ۚ لَّا مُبَدِّلَ لِكَلِمَٰتِهِۦ ۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ
﴿١١٥﴾ وَإِن تُطِعْ أَكْثَرَ مَن فِى ٱلْأَرْضِ يُضِلُّوكَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ ۚ إِن
يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ وَإِنْ هُمْ إِلَّا يَخْرُصُونَ ﴿١١٦﴾ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ
أَعْلَمُ مَن يَضِلُّ عَن سَبِيلِهِۦ ۖ وَهُوَ أَعْلَمُ بِٱلْمُهْتَدِينَ ﴿١١٧﴾ فَكُلُوا۟
مِمَّا ذُكِرَ ٱسْمُ ٱللَّهِ عَلَيْهِ إِن كُنتُم بِـَٔايَٰتِهِۦ مُؤْمِنِينَ ﴿١١٨﴾

(111) Kuma Mu din nan da a ce lalle za Mu saukar musu da mala'iku, kuma matattu su yi musu magana, kuma Mu tattaro musu komai a gabansu, to da ba za su taba yin imani ba, sai dai idan Allah Ya ga dama, amma yawancinsu suna jahilta ne

(112) Kuma kamar haka ne Muka sanya wa kowane annabi makiya daga shaidanun mutane da aljannu, sashinsu yana kimsa wa wani sashi kayataccen zance, don rudi. Kuma da Ubangijinka Ya ga dama da ba su aikata haka ba; don haka ka kyale su da irin abin da suke kagowa

(113) Don kuma zukatan wadanda ba su yi imani da lahira ba su karkata zuwa gare shi, kuma su yarda da shi (rudin) kuma su ci gaba da kago abin da suke kagowa

(114) ((Ka ce) "Shin wanin Allah zan nema a matsayin mai yi mana hukunci, alhalin Shi ne wanda Ya saukar muku da littafi mai bayani dalla-dalla?" Wadanda Muka ba su littafi kuwa suna sane da cewa, lalle shi saukakke ne daga Ubangijinka da gaskiya; don haka lalle kada ka kasance daga cikin masu kokwanto

(115) Kuma kalmomin Ubangijinka cike suke da gaskiya da adalci. Babu kuma mai canza kalmominsa; kuma Shi ne Mai ji, Masani

(116) Kuma in da za ka yi biyayya ga mafiya yawan wadanda suke a bayan kasa to za su batar da kai daga tafarkin Allah. Babu abin da suke bi face zato, kuma ba abin da suke yi face karya

(117) Lalle Ubangijinka Shi ne Mafi sanin wadanda suke bace wa tafarkinsa, kuma Shi ne Mafi sanin shiryayyu

(118) To ku ci abin da aka ambaci sunan Allah a kansa (lokacin yankansa), in har kun kasance masu imani da ayoyinsa

وَمَا لَكُمْ أَلَّا تَأْكُلُوا۟ مِمَّا ذُكِرَ ٱسْمُ ٱللَّهِ عَلَيْهِ وَقَدْ فَصَّلَ
لَكُم مَّا حَرَّمَ عَلَيْكُمْ إِلَّا مَا ٱضْطُرِرْتُمْ إِلَيْهِ ۗ وَإِنَّ كَثِيرًا
لَّيُضِلُّونَ بِأَهْوَآئِهِم بِغَيْرِ عِلْمٍ ۗ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعْلَمُ بِٱلْمُعْتَدِينَ
﴿١١٩﴾ وَذَرُوا۟ ظَٰهِرَ ٱلْإِثْمِ وَبَاطِنَهُۥٓ ۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكْسِبُونَ ٱلْإِثْمَ
سَيُجْزَوْنَ بِمَا كَانُوا۟ يَقْتَرِفُونَ ﴿١٢٠﴾ وَلَا تَأْكُلُوا۟ مِمَّا لَمْ
يُذْكَرِ ٱسْمُ ٱللَّهِ عَلَيْهِ وَإِنَّهُۥ لَفِسْقٌ ۗ وَإِنَّ ٱلشَّيَٰطِينَ لَيُوحُونَ
إِلَىٰٓ أَوْلِيَآئِهِمْ لِيُجَٰدِلُوكُمْ ۖ وَإِنْ أَطَعْتُمُوهُمْ إِنَّكُمْ لَمُشْرِكُونَ
﴿١٢١﴾ أَوَمَن كَانَ مَيْتًا فَأَحْيَيْنَٰهُ وَجَعَلْنَا لَهُۥ نُورًا يَمْشِى بِهِۦ
فِى ٱلنَّاسِ كَمَن مَّثَلُهُۥ فِى ٱلظُّلُمَٰتِ لَيْسَ بِخَارِجٍ مِّنْهَا ۚ كَذَٰلِكَ
زُيِّنَ لِلْكَٰفِرِينَ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٢٢﴾ وَكَذَٰلِكَ جَعَلْنَا
فِى كُلِّ قَرْيَةٍ أَكَٰبِرَ مُجْرِمِيهَا لِيَمْكُرُوا۟ فِيهَا ۖ وَمَا
يَمْكُرُونَ إِلَّا بِأَنفُسِهِمْ وَمَا يَشْعُرُونَ ﴿١٢٣﴾ وَإِذَا جَآءَتْهُمْ
ءَايَةٌ قَالُوا۟ لَن نُّؤْمِنَ حَتَّىٰ نُؤْتَىٰ مِثْلَ مَآ أُوتِىَ رُسُلُ ٱللَّهِ ۘ ٱللَّهُ
أَعْلَمُ حَيْثُ يَجْعَلُ رِسَالَتَهُۥ ۗ سَيُصِيبُ ٱلَّذِينَ أَجْرَمُوا۟ صَغَارٌ
عِندَ ٱللَّهِ وَعَذَابٌ شَدِيدٌۢ بِمَا كَانُوا۟ يَمْكُرُونَ ﴿١٢٤﴾

(119) Kuma me ya sa ba za ku ci abin da aka ambaci sunan Allah a kansa ba, alhali Ya bayyana muku abin da Ya haramta muku, sai fa abin da kuka matsu game da shi[1]? Kuma lalle yawancinsu ba shakka suna ɓatar da waɗansu ne ta hanyar bin son zuciyarsu, ba tare da ilimi ba. Lalle Ubangijinka Shi ne Mafi sanin masu ƙetare iyaka

(120) Kuma ku bar (aikata) laifuka na sarari da na ɓoye. Haƙiƙa waɗanda suke aikata saɓo, za a saka musu da irin abin da suke aikatawa

(121) Kuma kada ku ci daga abin da ba a ambaci sunan Allah a kansa ba, kuma lalle shi tabbas fasiƙanci ne. Haƙiƙa shaiɗanu tabbas suna kimsa wa masoyansu, don su yi jayayya da ku; idan kuwa kuka bi su to lalle tabbas ku mushirikai ne.

(122) Shin yanzu wanda ya kasance matacce (kafiri), sai Muka rayar da shi, kuma Muka sanya masa haske (na shiriya), yana tafiya da shi cikin mutane, (yanzu) zai zama kamar wanda yake cikin duhu (na kafirci), ta yadda ba zai iya fita daga cikinsa ba? Kamar haka ne aka ƙawata wa kafirai abin da suka kasance suna aikatawa

(123) Kuma kamar haka ne a cikin kowace ƙasa Muka sanya manyan masu laifinta, don su yi makirci a cikinta; kuma ba wanda suke ƙulla wa makirci sai kawunansu, amma su ba sa jin (haka)

(124) Kuma idan wata aya ta zo musu, sai su ce: "Ba za mu yi imani ba, har sai an ba mu kwatankwacin abin da aka ba wa manzannin Allah." Ai Allah Shi ne Mafi sanin inda ya dace Ya sanya manzancinsa. Da sannu ƙasƙanci daga Allah zai auka wa waɗanda suka aikata manyan laifuka da kuma azaba mai tsanani, saboda abin da suka kasance suna shiryawa na makirci

(1) A halin larura an halatta wa Musulmi ya ci abin da aka haramta masa gwargwadon wannan larurar kaɗai.

فَمَن يُرِدِ ٱللَّهُ أَن يَهۡدِيَهُۥ يَشۡرَحۡ صَدۡرَهُۥ لِلۡإِسۡلَٰمِۖ وَمَن
يُرِدۡ أَن يُضِلَّهُۥ يَجۡعَلۡ صَدۡرَهُۥ ضَيِّقًا حَرَجًا كَأَنَّمَا
يَصَّعَّدُ فِي ٱلسَّمَآءِۚ كَذَٰلِكَ يَجۡعَلُ ٱللَّهُ ٱلرِّجۡسَ عَلَى ٱلَّذِينَ
لَا يُؤۡمِنُونَ ﴿١٢٥﴾ وَهَٰذَا صِرَٰطُ رَبِّكَ مُسۡتَقِيمٗاۗ قَدۡ فَصَّلۡنَا
ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَذَّكَّرُونَ ﴿١٢٦﴾ لَهُمۡ دَارُ ٱلسَّلَٰمِ عِندَ
رَبِّهِمۡۖ وَهُوَ وَلِيُّهُم بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ﴿١٢٧﴾ وَيَوۡمَ يَحۡشُرُهُمۡ
جَمِيعٗا يَٰمَعۡشَرَ ٱلۡجِنِّ قَدِ ٱسۡتَكۡثَرۡتُم مِّنَ ٱلۡإِنسِۖ وَقَالَ
أَوۡلِيَآؤُهُم مِّنَ ٱلۡإِنسِ رَبَّنَا ٱسۡتَمۡتَعَ بَعۡضُنَا بِبَعۡضٖ وَبَلَغۡنَآ
أَجَلَنَا ٱلَّذِيٓ أَجَّلۡتَ لَنَاۚ قَالَ ٱلنَّارُ مَثۡوَىٰكُمۡ خَٰلِدِينَ فِيهَآ
إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُۚ إِنَّ رَبَّكَ حَكِيمٌ عَلِيمٞ ﴿١٢٨﴾ وَكَذَٰلِكَ نُوَلِّي
بَعۡضَ ٱلظَّٰلِمِينَ بَعۡضَۢا بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ﴿١٢٩﴾
يَٰمَعۡشَرَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِ أَلَمۡ يَأۡتِكُمۡ رُسُلٞ مِّنكُمۡ
يَقُصُّونَ عَلَيۡكُمۡ ءَايَٰتِي وَيُنذِرُونَكُمۡ لِقَآءَ يَوۡمِكُمۡ
هَٰذَاۚ قَالُواْ شَهِدۡنَا عَلَىٰٓ أَنفُسِنَاۖ وَغَرَّتۡهُمُ ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا
وَشَهِدُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡ أَنَّهُمۡ كَانُواْ كَٰفِرِينَ ﴿١٣٠﴾

(125) Sannan duk wanda Allah Ya yi nufin shiryar da shi, sai Ya yalwata ƙirjinsa ga karɓar Musulunci. Duk wanda kuwa Ya yi nufin Ya ɓatar da shi, sai Ya sanya ƙirjinsa a ƙuntace ainun kamar wanda yake yunƙurin hawa sama. Kamar haka ne Allah Yake sanya ɓata a kan waɗanda ba sa yin imani

(126) Kuma wannan shi ne tafarkin Ubangijinka miƙaƙƙe. Haƙiƙa Mun bayyana ayoyi ga mutanen da suke tuntuntuni

(127) Suna da gida na aminci a wurin Ubangijinsu, kuma Shi ne Majiɓincinsu, saboda abin da suka kasance suna aikatawa

(128) Kuma (ka tuna) ranar da zai tara su gaba ɗaya (Ya ce): "Ya ku jama'ar aljannu, haƙiƙa kun samu mabiya da yawa daga cikin mutane." Sai majiɓinta lamarinsu cikin mutane su ce: "Ya Ubangijinmu; mun dai daɗaɗa wa junanmu kuma mun kawo ƙarshen lokacin da Ka yanka mana." Sai Ya ce: "Wuta ita ce makomarku, za ku dawwama a cikinta, sai dai abin da Allah Ya ga dama." Lalle Ubangijinka Mai hikima ne, Mai yawan sani

(129) Kuma kamar haka ne Muke ɗora wani sashi na azzalumai a kan wani sashi, saboda abin da suka kasance suna aikatawa

(130) (Ya ku jama'ar aljannu da mutane, shin manzanni daga cikinku ba su zo muku ba, suna karanta muku ayoyina, kuma suna gargaɗin ku game da saduwarku da wannan yini?" Sai su ce: "Mun ba da shaida a kan kawunanmu;" rayuwar duniya kuma ta ruɗe su, kuma suka yi wa kansu shaidar cewa lalle su sun kasance kafirai

ذَٰلِكَ أَن لَّمْ يَكُن رَّبُّكَ مُهْلِكَ ٱلْقُرَىٰ بِظُلْمٍ وَأَهْلُهَا
غَٰفِلُونَ ﴿١٣١﴾ وَلِكُلٍّ دَرَجَٰتٌ مِّمَّا عَمِلُوا۟ ۚ وَمَا رَبُّكَ
بِغَٰفِلٍ عَمَّا يَعْمَلُونَ ﴿١٣٢﴾ وَرَبُّكَ ٱلْغَنِىُّ ذُو ٱلرَّحْمَةِ ۚ
إِن يَشَأْ يُذْهِبْكُمْ وَيَسْتَخْلِفْ مِنۢ بَعْدِكُم مَّا
يَشَآءُ كَمَآ أَنشَأَكُم مِّن ذُرِّيَّةِ قَوْمٍ ءَاخَرِينَ ﴿١٣٣﴾
إِنَّ مَا تُوعَدُونَ لَءَاتٍ ۖ وَمَآ أَنتُم بِمُعْجِزِينَ ﴿١٣٤﴾ قُلْ يَٰقَوْمِ
ٱعْمَلُوا۟ عَلَىٰ مَكَانَتِكُمْ إِنِّى عَٰمِلٌ ۖ فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ
مَن تَكُونُ لَهُۥ عَٰقِبَةُ ٱلدَّارِ ۚ إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿١٣٥﴾
وَجَعَلُوا۟ لِلَّهِ مِمَّا ذَرَأَ مِنَ ٱلْحَرْثِ وَٱلْأَنْعَٰمِ نَصِيبًا
فَقَالُوا۟ هَٰذَا لِلَّهِ بِزَعْمِهِمْ وَهَٰذَا لِشُرَكَآئِنَا ۖ فَمَا كَانَ
لِشُرَكَآئِهِمْ فَلَا يَصِلُ إِلَى ٱللَّهِ ۖ وَمَا كَانَ لِلَّهِ فَهُوَ
يَصِلُ إِلَىٰ شُرَكَآئِهِمْ ۗ سَآءَ مَا يَحْكُمُونَ ﴿١٣٦﴾ وَكَذَٰلِكَ
زَيَّنَ لِكَثِيرٍ مِّنَ ٱلْمُشْرِكِينَ قَتْلَ أَوْلَٰدِهِمْ
شُرَكَآؤُهُمْ لِيُرْدُوهُمْ وَلِيَلْبِسُوا۟ عَلَيْهِمْ دِينَهُمْ ۖ
وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا فَعَلُوهُ ۖ فَذَرْهُمْ وَمَا يَفْتَرُونَ ﴿١٣٧﴾

(131) Haka ta faru ne, saboda Ubangijinka bai zamanto Mai hallakar da wata alƙarya saboda kafircewarta ba, alhali mutanenta suna cikin gafala
(132) Kuma kowanne yana da nasa matsayi game da abin da suka aikata, kuma Ubangijinka bai zama Mai rafkana ba dangane da abin da suke aikatawa
(133) Kuma Ubangijinka Shi ne Mawadaci, Mai rahama. Idan Ya ga dama sai Ya tafiyar da ku, kuma Ya maye gurbinku da waɗanda Ya ga dama, kamar yadda Ya fare ku daga zurriyar waɗansu mutanen daban
(134) Lalle abin da ake yi Muku alƙawarinsa mai zuwa ne; kuma ku ba za ku iya kuɓucewa (daga azabarmu) ba
(135) Ka ce: "Ya ku mutanena, ku yi aiki a kan irin hanyarku, lalle ni ma mai yin aiki ne (kan hanyata); don haka da sannu za ku san wanda zai yi kyakkyawan ƙarshe. Lalle su dai azzalumai ba za su rabauta ba
(136) Kuma sun sanya wa Allah wani kaso cikin abin da Ya halitta na amfanin gona da dabbobin gida, sai suka rika cewa: "Wannan kaso na Allah ne", a riyawarsu, "Wannan kuma na gumakanmu ne;" sannan abin da ya kasance na gumakansu ba zai isa ga Allah ba; abin da kuwa ya kasance na Allah, to shi zai isa ga gumakansu. Abin da suke hukuntawa ya munana[1]
(137) Kuma kamar haka ne abokan tarayyarsu suka ƙawata wa yawancin mushirikai su dinga kashe 'ya'yansu, don su hallakar da su, kuma don su rikita musu addininsu. Kuma da Allah Ya ga dama da ba su aikata haka ba. To ka ƙyale su da irin abin da suke ƙagawa

(1) Mushirikan Larabawa sukan kasa amfanin gonarsu da dabbobinsu kaso biyu, kaso ɗaya su ce na Allah ne, kaso na biyun kuma su ce na gumakansu ne. To idan kason gumakansu ya shiga cikin kason Allah sai su dawo da shi wurinsu,amma idan kason da suka ware wa Allah ya shiga na gumakansu ba za su dawo da shi ba.

وَقَالُوا۟ هَٰذِهِۦٓ أَنْعَٰمٌ وَحَرْثٌ حِجْرٌ لَّا يَطْعَمُهَآ إِلَّا مَن نَّشَآءُ
بِزَعْمِهِمْ وَأَنْعَٰمٌ حُرِّمَتْ ظُهُورُهَا وَأَنْعَٰمٌ لَّا يَذْكُرُونَ
ٱسْمَ ٱللَّهِ عَلَيْهَا ٱفْتِرَآءً عَلَيْهِ ۚ سَيَجْزِيهِم بِمَا كَانُوا۟
يَفْتَرُونَ ﴿١٣٨﴾ وَقَالُوا۟ مَا فِى بُطُونِ هَٰذِهِ ٱلْأَنْعَٰمِ خَالِصَةٌ
لِّذُكُورِنَا وَمُحَرَّمٌ عَلَىٰٓ أَزْوَٰجِنَا ۖ وَإِن يَكُن مَّيْتَةً
فَهُمْ فِيهِ شُرَكَآءُ ۚ سَيَجْزِيهِمْ وَصْفَهُمْ ۚ إِنَّهُۥ حَكِيمٌ
عَلِيمٌ ﴿١٣٩﴾ قَدْ خَسِرَ ٱلَّذِينَ قَتَلُوٓا۟ أَوْلَٰدَهُمْ سَفَهًۢا بِغَيْرِ
عِلْمٍ وَحَرَّمُوا۟ مَا رَزَقَهُمُ ٱللَّهُ ٱفْتِرَآءً عَلَى ٱللَّهِ ۚ قَدْ ضَلُّوا۟
وَمَا كَانُوا۟ مُهْتَدِينَ ﴿١٤٠﴾ * وَهُوَ ٱلَّذِىٓ أَنشَأَ جَنَّٰتٍ
مَّعْرُوشَٰتٍ وَغَيْرَ مَعْرُوشَٰتٍ وَٱلنَّخْلَ وَٱلزَّرْعَ مُخْتَلِفًا
أُكُلُهُۥ وَٱلزَّيْتُونَ وَٱلرُّمَّانَ مُتَشَٰبِهًا وَغَيْرَ مُتَشَٰبِهٍ ۚ
كُلُوا۟ مِن ثَمَرِهِۦٓ إِذَآ أَثْمَرَ وَءَاتُوا۟ حَقَّهُۥ يَوْمَ حَصَادِهِۦ ۖ
وَلَا تُسْرِفُوٓا۟ ۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلْمُسْرِفِينَ ﴿١٤١﴾ وَمِنَ ٱلْأَنْعَٰمِ
حَمُولَةً وَفَرْشًا ۚ كُلُوا۟ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ وَلَا تَتَّبِعُوا۟
خُطُوَٰتِ ٱلشَّيْطَٰنِ ۚ إِنَّهُۥ لَكُمْ عَدُوٌّ مُّبِينٌ ﴿١٤٢﴾


(138) Kuma suka ce: "Waɗannan dabbobi na gida da kuma amfanin gona haramtattu ne, ba wanda zai ci su sai wanda muka ga dama," a riyawarsu. Waɗansu dabbobin kuma an haramta hawansu, waɗansu dabbobin kuma ba sa ambaton sunan Allah a kansu (yayin yankan su), don kawai su yi masa ƙage. Da sannu zai yi musu sakamakon abin da suka kasance suna ƙagawa

(139) Kuma suka ce: "Abin da yake cikin waɗannan dabbobi, a keɓance yake ga mazajenmu, amma haramun ne ga matayenmu." Idan kuma ya zamo mushe, to su duka sai su yi tarayya a kansa. Da sannu (Allah) zai yi musu sakayyar wannan abin da suka siffanta. Lalle Shi Mai hikima ne, Mai yawan sani

(140) Haƙiƙa waɗannan da suka kashe 'ya'yansu don wauta, ba tare da ilimi ba sun taɓe, kuma suka haramta wa kansu abin da Allah Ya arzuta su da shi, don ƙage ga Allah. Haƙiƙa sun ɓata, kuma ba su kasance shiryayyu ba

(141) Kuma Shi ne Wanda Ya halicci lambuna waɗanda suke da tsirrai masu yaɗo da marasa yaɗo da kuma dabino da shukoki waɗanda suka sha bamban da juna wajen ɗanɗanonsu, da kuma zaitun da ruman, mai kama da juna, da wanda ba ya kama da juna. Ku ci daga 'ya'yansa, idan ya yi 'ya'ya, kuma ku bayar da zakkarsa a ranar girbinsa, kuma kada ku yi almubazzaranci. Lalle Shi (Allah) ba Ya son masu almubazzaranci

(142) Daga cikin dabbobin gida kuma akwai masu ɗaukan kaya da kuma ƙanana. Ku ci daga abin da Allah Ya arzuta ku da shi, kuma kada ku bi hanyoyin Shaiɗan. Lalle shi maƙiyi ne mai bayyana ƙiyayya a gare kui



ثَمَٰنِيَةَ أَزۡوَٰجٖۖ مِّنَ ٱلضَّأۡنِ ٱثۡنَيۡنِ وَمِنَ ٱلۡمَعۡزِ ٱثۡنَيۡنِۗ
قُلۡ ءَآلذَّكَرَيۡنِ حَرَّمَ أَمِ ٱلۡأُنثَيَيۡنِ أَمَّا ٱشۡتَمَلَتۡ عَلَيۡهِ
أَرۡحَامُ ٱلۡأُنثَيَيۡنِۖ نَبِّـُٔونِي بِعِلۡمٍ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ١٤٣
وَمِنَ ٱلۡإِبِلِ ٱثۡنَيۡنِ وَمِنَ ٱلۡبَقَرِ ٱثۡنَيۡنِۗ قُلۡ ءَآلذَّكَرَيۡنِ
حَرَّمَ أَمِ ٱلۡأُنثَيَيۡنِ أَمَّا ٱشۡتَمَلَتۡ عَلَيۡهِ أَرۡحَامُ ٱلۡأُنثَيَيۡنِۖ
أَمۡ كُنتُمۡ شُهَدَآءَ إِذۡ وَصَّىٰكُمُ ٱللَّهُ بِهَٰذَاۚ فَمَنۡ
أَظۡلَمُ مِمَّنِ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبٗا لِّيُضِلَّ ٱلنَّاسَ بِغَيۡرِ
عِلۡمٍۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٤٤ قُل لَّآ أَجِدُ
فِي مَآ أُوحِيَ إِلَيَّ مُحَرَّمًا عَلَىٰ طَاعِمٖ يَطۡعَمُهُۥٓ إِلَّآ أَن يَكُونَ
مَيۡتَةً أَوۡ دَمٗا مَّسۡفُوحًا أَوۡ لَحۡمَ خِنزِيرٖ فَإِنَّهُۥ رِجۡسٌ أَوۡ
فِسۡقًا أُهِلَّ لِغَيۡرِ ٱللَّهِ بِهِۦۚ فَمَنِ ٱضۡطُرَّ غَيۡرَ بَاغٖ وَلَا عَادٖ
فَإِنَّ رَبَّكَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٤٥ وَعَلَى ٱلَّذِينَ هَادُواْ حَرَّمۡنَا
كُلَّ ذِي ظُفُرٖۖ وَمِنَ ٱلۡبَقَرِ وَٱلۡغَنَمِ حَرَّمۡنَا عَلَيۡهِمۡ
شُحُومَهُمَآ إِلَّا مَا حَمَلَتۡ ظُهُورُهُمَآ أَوِ ٱلۡحَوَايَآ أَوۡ مَا ٱخۡتَلَطَ
بِعَظۡمٖۚ ذَٰلِكَ جَزَيۡنَٰهُم بِبَغۡيِهِمۡۖ وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَ ١٤٦

(143) (Dabbobin) nau'i takwas ne, daga tumaki akwai jinsi biyu, haka kuma daga awaki akwai jinsi biyu. Ka ce: "Shin mazan biyu ne Ya haramta ko kuma matan biyu ko kuma abin da yake cikin mahaifar matan biyu? Ku ba ni labari da ilimi in kun kasance ku masu gaskiya ne."
(144) Haka kuma rakuma akwai jinsi biyu, daga cikin shanu ma akwai jinsi biyu. Ka ce: "Shin mazan guda biyu Ya haramta ko matan biyu ko kuma abin da yake cikin mahaifar matan biyu ya haramta ko kuma kun zama shaidu yayin da Allah Ya yi muku wasicci da wannan abin?" To ba wanda ya fi zaluntar kansa fiye da wanda ya kirkiri karya, ya jingina wa Allah don ya batar da mutane ba tare da ilimi ba. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutane azzalumai
(145) Ka ce: "Daga cikin abin da aka saukar mini na manzanci ban samu wani abinci da aka haramta cinsa ba, sai fa idan ya zamo mushe ne ko jini mai kwarara, ko kuma naman alade, to lalle wannan kazanta ne, ko kuma abin da ya zamo fasikanci ne wanda aka yanka shi ba da sunan Allah ba." Sannan wanda ya matsu, ba tare da shisshigi ba, kuma ba yana mai ketare iyaka ba, to lalle Ubangijinka Mai gafara ne, Mai jin kai
(146) Kuma Mun haramta wa Yahudawa duk wata dabba mai kofato; daga shanu da tumaki kuwa Mun haramta musu kitsensu, sai abin da gadon bayansu yake dauke da shi ko kayan cikinsu ko abin da ya cakuɗu da kashi[1]. Wannan Mun Yi musu sakamako da shi ne saboda zaluncinsu; kuma lalle Mu tabbas Masu gaskiya ne

(1) Watau an haramta musu kitsen shanu da tumaki sai dai kitsen da ke gadon bayan waɗannan dabbobi ko wanda yake tare da kaya ciki ko wanda ya haɗe da kashi.

فَإِن كَذَّبُوكَ فَقُل رَّبُّكُمْ ذُو رَحْمَةٍ وَٰسِعَةٍ وَلَا يُرَدُّ
بَأْسُهُۥ عَنِ ٱلْقَوْمِ ٱلْمُجْرِمِينَ ﴿١٤٧﴾ سَيَقُولُ ٱلَّذِينَ أَشْرَكُوا۟
لَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَآ أَشْرَكْنَا وَلَآ ءَابَآؤُنَا وَلَا حَرَّمْنَا مِن شَىْءٍ ۚ
كَذَٰلِكَ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ حَتَّىٰ ذَاقُوا۟ بَأْسَنَا ۗ
قُلْ هَلْ عِندَكُم مِّنْ عِلْمٍ فَتُخْرِجُوهُ لَنَآ ۖ إِن تَتَّبِعُونَ إِلَّا
ٱلظَّنَّ وَإِنْ أَنتُمْ إِلَّا تَخْرُصُونَ ﴿١٤٨﴾ قُلْ فَلِلَّهِ ٱلْحُجَّةُ ٱلْبَٰلِغَةُ ۖ
فَلَوْ شَآءَ لَهَدَىٰكُمْ أَجْمَعِينَ ﴿١٤٩﴾ قُلْ هَلُمَّ شُهَدَآءَكُمُ
ٱلَّذِينَ يَشْهَدُونَ أَنَّ ٱللَّهَ حَرَّمَ هَٰذَا ۖ فَإِن شَهِدُوا۟ فَلَا تَشْهَدْ
مَعَهُمْ ۚ وَلَا تَتَّبِعْ أَهْوَآءَ ٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا وَٱلَّذِينَ
لَا يُؤْمِنُونَ بِٱلْءَاخِرَةِ وَهُم بِرَبِّهِمْ يَعْدِلُونَ ﴿١٥٠﴾ ۞ قُلْ
تَعَالَوْا۟ أَتْلُ مَا حَرَّمَ رَبُّكُمْ عَلَيْكُمْ ۖ أَلَّا تُشْرِكُوا۟
بِهِۦ شَيْـًٔا ۖ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَٰنًا ۖ وَلَا تَقْتُلُوٓا۟ أَوْلَٰدَكُم
مِّنْ إِمْلَٰقٍ نَّحْنُ نَرْزُقُكُمْ وَإِيَّاهُمْ ۖ وَلَا تَقْرَبُوا۟ ٱلْفَوَٰحِشَ
مَا ظَهَرَ مِنْهَا وَمَا بَطَنَ ۖ وَلَا تَقْتُلُوا۟ ٱلنَّفْسَ ٱلَّتِى حَرَّمَ ٱللَّهُ
إِلَّا بِٱلْحَقِّ ۚ ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿١٥١﴾

(147) Sannan idan sun ƙaryata ka, to ka ce: "Ubangijinku Ma'abocin rahama mayalwaciya ne. Kuma ba a iya mayar da azabarsa daga mutanen da suke masu laifi."
(148) Waɗanda suke yin shirka za su ce: "Da Allah Ya ga dama, da ba mu yi shirka ba, haka iyayenmu ma da ba su yi ba, kuma da ba mu haramta wani abu ba." Kamar haka ne waɗanda suka gabace su suka ƙaryata (manzanni), har sai da suka ɗanɗani azabarmu. Ka ce: "Shin kuna da wata hujja ce da za ku fito mana da ita? Ba fa abin da kuke bi sai zato, kuma ku (ba a kan komai kuke ba) face shaci-faɗi."
(149) Ka ce: "To a wurin Allah ne cikakkiyar hujja take; kuma da Ya ga dama, tabbas da Ya shiryar da ku gaba ɗaya."
(150) Ka ce: "Ku kawo shaidunku waɗanda za su ba da shaidar cewa, Allah Shi Ya haramta wannan." Sannan idan har sun ba da shaidar, to kai kada ka bayar da shaida tare da su. Kuma kada ka bi soye-soyen zukatan waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu, waɗanda kuma ba sa yin imani da ranar lahira, su ne kuwa masu daidaita Ubangijinsu (da wani abu)
(151) Ka ce: "Ku taho in karanta muku abin da Ubangijinku Ya haramta muku; kada ku haɗa Shi da wani; kuma ku kyautata wa mahaifa; kuma kar ku kashe 'ya'yanku saboda talauci; Mu ne za Mu arzuta ku har da su; kuma kada ku kusanci munanan (ayyuka) na sarari da na ɓoye; kuma kada ku kashe ran da Allah Ya haramta (a kashe shi), sai idan da wani hakki. Wannan shi ne abin da (Allah) Ya yi muku wasiyya da shi, don ku zamo masu hankali

وَلَا تَقْرَبُوا۟ مَالَ ٱلْيَتِيمِ إِلَّا بِٱلَّتِى هِىَ أَحْسَنُ حَتَّىٰ يَبْلُغَ أَشُدَّهُۥ ۚ
وَأَوْفُوا۟ ٱلْكَيْلَ وَٱلْمِيزَانَ بِٱلْقِسْطِ ۖ لَا نُكَلِّفُ نَفْسًا إِلَّا
وُسْعَهَا ۖ وَإِذَا قُلْتُمْ فَٱعْدِلُوا۟ وَلَوْ كَانَ ذَا قُرْبَىٰ ۖ وَبِعَهْدِ
ٱللَّهِ أَوْفُوا۟ ۚ ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَذَكَّرُونَ ﴿١٥٢﴾
وَأَنَّ هَٰذَا صِرَٰطِى مُسْتَقِيمًا فَٱتَّبِعُوهُ ۖ وَلَا تَتَّبِعُوا۟ ٱلسُّبُلَ
فَتَفَرَّقَ بِكُمْ عَن سَبِيلِهِۦ ۚ ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمْ
تَتَّقُونَ ﴿١٥٣﴾ ثُمَّ ءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ تَمَامًا عَلَى ٱلَّذِىٓ
أَحْسَنَ وَتَفْصِيلًا لِّكُلِّ شَىْءٍ وَهُدًى وَرَحْمَةً لَّعَلَّهُم بِلِقَآءِ
رَبِّهِمْ يُؤْمِنُونَ ﴿١٥٤﴾ وَهَٰذَا كِتَٰبٌ أَنزَلْنَٰهُ مُبَارَكٌ فَٱتَّبِعُوهُ
وَٱتَّقُوا۟ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿١٥٥﴾ أَن تَقُولُوٓا۟ إِنَّمَآ أُنزِلَ ٱلْكِتَٰبُ
عَلَىٰ طَآئِفَتَيْنِ مِن قَبْلِنَا وَإِن كُنَّا عَن دِرَاسَتِهِمْ لَغَٰفِلِينَ
﴿١٥٦﴾ أَوْ تَقُولُوا۟ لَوْ أَنَّآ أُنزِلَ عَلَيْنَا ٱلْكِتَٰبُ لَكُنَّآ أَهْدَىٰ
مِنْهُمْ ۚ فَقَدْ جَآءَكُم بَيِّنَةٌ مِّن رَّبِّكُمْ وَهُدًى وَرَحْمَةٌ ۚ
فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَصَدَفَ عَنْهَا ۗ سَنَجْزِى ٱلَّذِينَ
يَصْدِفُونَ عَنْ ءَايَٰتِنَا سُوٓءَ ٱلْعَذَابِ بِمَا كَانُوا۟ يَصْدِفُونَ ﴿١٥٧﴾

(152) "Kuma kada ku kusanci dukiyar maraya sai da kyakkyawar niyya, har sai ƙarfinsa ya kawo; kuma ku cika ma'auni na mudu da na nauyi bisa adalci; ba ma ɗora wa rai sai abin da zai iya. Kuma idan za ku yi magana to ku yi adalci, ko da kuwa a kan ɗan'uwa ne na kusa; kuma lalle ku cika alƙawarin Allah. Wannan ne abin da (Allah) Yake yi muku wasicci da shi, don ku wa'azantu."

(153) "Kuma lalle wannan shi ne tafarkina miƙaƙƙe, don haka ku bi shi; kada ku bi waɗansu hanyoyi daban, sai su raba ku da hanyarsa. Wannan shi ne abin da (Allah) Yake yi muku wasicci da shi don ku samu taƙawa."

(154) Sannan Muka bai wa Musa littafin (Attaura) don cika (ni'imarmu) ga wanda ya kyautata, kuma bayani ne na kowane irin abu, kuma shiriya ne da rahama, domin su zamo masu imani da haɗuwa da Ubangijinsu

(155) Kuma wannan Littafi (Alƙur'ani) Mun saukar da shi, yana mai cike da albarka, don haka ku bi shi, kuma ku kiyaye dokokin (Allah), domin a ji ƙan ku

(156) Don kada ku ce: "Kungiya biyu ne waɗanda suka gabace mu kawai aka saukar wa da Littafi, mu kuma ba mu san komai game da abin da suka karanta ba."

(157) Ko kuma ku ce: "In da mu aka saukar wa da littafin, to da lalle mun fi su shiryuwa." To ai haƙiƙa hujja ta riga ta zo muku daga Ubangijinku, da kuma shiriya da rahama; don haka babu wanda ya fi zalunci fiye da wanda ya ƙaryata ayoyin Allah, kuma ya yi watsi da su. Da sannu za Mu saka wa waɗanda suke bijire wa ayoyinmu da mummunar azaba, saboda bijirewar da suke yi

هَلْ يَنظُرُونَ إِلَّآ أَن تَأْتِيَهُمُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ أَوْ يَأْتِىَ رَبُّكَ أَوْ يَأْتِىَ بَعْضُ
ءَايَٰتِ رَبِّكَ ۗ يَوْمَ يَأْتِى بَعْضُ ءَايَٰتِ رَبِّكَ لَا يَنفَعُ نَفْسًا إِيمَٰنُهَا
لَمْ تَكُنْ ءَامَنَتْ مِن قَبْلُ أَوْ كَسَبَتْ فِىٓ إِيمَٰنِهَا خَيْرًا ۗ قُلِ ٱنتَظِرُوٓا۟
إِنَّا مُنتَظِرُونَ ﴿١٥٨﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ فَرَّقُوا۟ دِينَهُمْ وَكَانُوا۟ شِيَعًا لَّسْتَ
مِنْهُمْ فِى شَىْءٍ ۚ إِنَّمَآ أَمْرُهُمْ إِلَى ٱللَّهِ ثُمَّ يُنَبِّئُهُم بِمَا كَانُوا۟ يَفْعَلُونَ
﴿١٥٩﴾ مَن جَآءَ بِٱلْحَسَنَةِ فَلَهُۥ عَشْرُ أَمْثَالِهَا ۖ وَمَن جَآءَ بِٱلسَّيِّئَةِ
فَلَا يُجْزَىٰٓ إِلَّا مِثْلَهَا وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿١٦٠﴾ قُلْ إِنَّنِى هَدَىٰنِى رَبِّىٓ
إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ دِينًا قِيَمًا مِّلَّةَ إِبْرَٰهِيمَ حَنِيفًا ۚ وَمَا كَانَ
مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿١٦١﴾ قُلْ إِنَّ صَلَاتِى وَنُسُكِى وَمَحْيَاىَ وَمَمَاتِى لِلَّهِ
رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٦٢﴾ لَا شَرِيكَ لَهُۥ ۖ وَبِذَٰلِكَ أُمِرْتُ وَأَنَا۠ أَوَّلُ ٱلْمُسْلِمِينَ
﴿١٦٣﴾ قُلْ أَغَيْرَ ٱللَّهِ أَبْغِى رَبًّا وَهُوَ رَبُّ كُلِّ شَىْءٍ ۚ وَلَا تَكْسِبُ كُلُّ
نَفْسٍ إِلَّا عَلَيْهَا ۚ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٌ وِزْرَ أُخْرَىٰ ۚ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُم
مَّرْجِعُكُمْ فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ فِيهِ تَخْتَلِفُونَ ﴿١٦٤﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى جَعَلَكُمْ
خَلَٰٓئِفَ ٱلْأَرْضِ وَرَفَعَ بَعْضَكُمْ فَوْقَ بَعْضٍ دَرَجَٰتٍ لِّيَبْلُوَكُمْ فِى
مَآ ءَاتَىٰكُمْ ۗ إِنَّ رَبَّكَ سَرِيعُ ٱلْعِقَابِ وَإِنَّهُۥ لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٦٥﴾

(158) Sannan ba abin da suke sauraro face mala'iku su zo musu ko Ubangijinka Ya zo musu ko wani sashi na ayoyin Ubangijinka su zo. Ranar da wasu daga ayoyin Ubangijinka za su zo, to babu wani rai da imaninsa zai yi amfani, idan a da can bai yi imani ba ko bai yi aikin alheri ba cikin imaninsa. Ka ce: "Ku jira, mu ma masu jira ne."

(159) Lalle waɗanda suka rarraba addininsu kuma suka kasance ƙungiya-ƙungiya, to ba ruwanka da su. Al'amarinsu yana ga Allah ne kawai, sannan zai ba su labarin abin da suka kasance suna aikatawa

(160) Wanda ya zo da kyakkyawan aiki ɗaya, to yana da ninkin ladansa goma; wanda kuwa ya zo da mummuna ɗaya, to ba za a saka masa ba sai daidai da shi, ba kuma za a zalunce su ba

(161) Ka ce: "Lalle ni, Ubangijina Ya shiryar da ni zuwa ga tafarki madaidaici, shi ne addini miƙaƙƙe, addinin Ibrahimu wanda ya karkace wa ɓarna, kuma bai zama daga masu shirka ba."

(162) Ka ce: "Lalle sallata da yankana da rayuwata da mutuwata, duk na Allah ne Ubangijin talikai

(163) "Ba Shi da abokin tarayya; kuma da hakan aka umarce ni, kuma ni ne farkon Musulmai."

(164) Ka ce: "Yanzu wanin Allah zan riƙa a matsayin ubangiji, alhalin kuwa Shi ne Ubangijin komai? Kuma ba wani rai da zai aikata wani abu face sai don kansa. Kuma ba wani rai da zai ɗauki laifin wani rai. Sannan kuma zuwa ga Ubangijinku ne makomarku take, sai Ya ba ku labarin abin da kuka kasance kuna saɓani a game da shi

(165) "Kuma Shi ne Ya sanya ku halifofi a bayan ƙasa, kuma Ya ɗaukaka darajar wasunku a kan wasu, don Ya jarrabe ku game da abin da Ya ba ku. Lalle Ubangijinka Mai gaggawar uƙuba ne, kuma lalle Shi tabbas Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai."

Sura A'araf

سُورَةُ الأَعۡرَافِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓمٓصٓ ﴿١﴾ كِتَٰبٌ أُنزِلَ إِلَيۡكَ فَلَا يَكُن فِي صَدۡرِكَ حَرَجٞ مِّنۡهُ
لِتُنذِرَ بِهِۦ وَذِكۡرَىٰ لِلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿٢﴾ ٱتَّبِعُواْ مَآ أُنزِلَ إِلَيۡكُم
مِّن رَّبِّكُمۡ وَلَا تَتَّبِعُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَۗ قَلِيلٗا مَّا تَذَكَّرُونَ
﴿٣﴾ وَكَم مِّن قَرۡيَةٍ أَهۡلَكۡنَٰهَا فَجَآءَهَا بَأۡسُنَا بَيَٰتًا أَوۡ هُمۡ
قَآئِلُونَ ﴿٤﴾ فَمَا كَانَ دَعۡوَىٰهُمۡ إِذۡ جَآءَهُم بَأۡسُنَآ إِلَّآ أَن قَالُوٓاْ
إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ﴿٥﴾ فَلَنَسۡـَٔلَنَّ ٱلَّذِينَ أُرۡسِلَ إِلَيۡهِمۡ وَلَنَسۡـَٔلَنَّ
ٱلۡمُرۡسَلِينَ ﴿٦﴾ فَلَنَقُصَّنَّ عَلَيۡهِم بِعِلۡمٖ وَمَا كُنَّا غَآئِبِينَ ﴿٧﴾
وَٱلۡوَزۡنُ يَوۡمَئِذٍ ٱلۡحَقُّۚ فَمَن ثَقُلَتۡ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ
ٱلۡمُفۡلِحُونَ ﴿٨﴾ وَمَنۡ خَفَّتۡ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓاْ
أَنفُسَهُم بِمَا كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَظۡلِمُونَ ﴿٩﴾ وَلَقَدۡ مَكَّنَّٰكُمۡ
فِي ٱلۡأَرۡضِ وَجَعَلۡنَا لَكُمۡ فِيهَا مَعَٰيِشَۗ قَلِيلٗا مَّا تَشۡكُرُونَ
﴿١٠﴾ وَلَقَدۡ خَلَقۡنَٰكُمۡ ثُمَّ صَوَّرۡنَٰكُمۡ ثُمَّ قُلۡنَا لِلۡمَلَٰٓئِكَةِ
ٱسۡجُدُواْ لِأٓدَمَ فَسَجَدُوٓاْ إِلَّآ إِبۡلِيسَ لَمۡ يَكُن مِّنَ ٱلسَّٰجِدِينَ ﴿١١﴾

(1) ALIF LAAM MIIM SAAD[1]
(2) (Wannan) Littafi ne da aka saukar maka, don haka kada wani ƙunci ya kasance a ƙirjinka a sanadiyyarsa, don ka yi gargaɗi da shi, kuma da tunatarwa ga muminai
(3) Ku bi abin da aka saukar muku daga Ubangijinku, kada kuma ku bi wasu masoya ba shi ba. Kaɗan ne ƙwarai kuke wa'azantuwa
(4) Kuma nawa-nawa ne daga cikin alƙaryu waɗanda Muka (nufi) halaka su, sai azabar mu ta zo musu da daddare ko lokacin da suke barcin ƙailula?
(5) Sannan ba abin da suke faɗa, lokacin da azabarmu ta zo musu sai cewa: "Lalle mu mun kasance azzalumai."
(6) To lalle tabbas sai Mun tambayi waɗanda aka aiko musu manzanni, kuma lalle tabbas, sai mun tambayi manzannin (su kansu)
(7) Kuma lalle za Mu ba su labarin (komai) da ilimi; kuma ba Mu zamanto ba ma nan ba
(8) Awo kuma a wannan ranar gaskiya ne. Don haka duk wanda ma'aunansa suka yi nauyi, to waɗannan su ne masu rabauta
(9)Wanda kuwa ma'aunansa suka yi sakayau, to waɗannan su ne waɗanda suka yi hasarar kawunansu, saboda abin da suka kasance suna yi na zalunci da ayoyinmu
(10) Kuma lalle haƙiƙa Mun kafa ku a bayan ƙasa, kuma Muka sanya muku wuraren rayuwa a cikinta. Kaɗan ne ƙwarai kuke godiya
(11) Kuma lalle haƙiƙa Mun halicce ku, sannan kuma Muka suranta ku; sannan Muka ce wa mala'iku: "Ku yi sujjada ga Adamu," sai suka yi sujjada, sai Iblis ne kaɗai bai kasance cikin masu sujjada ba

(1) Duba Suratul Baƙara aya ta 1, hashiya ta 8.

قَالَ مَا مَنَعَكَ أَلَّا تَسْجُدَ إِذْ أَمَرْتُكَ ۖ قَالَ أَنَا۠ خَيْرٌ مِّنْهُ خَلَقْتَنِى مِن نَّارٍ
وَخَلَقْتَهُۥ مِن طِينٍ ﴿١٢﴾ قَالَ فَٱهْبِطْ مِنْهَا فَمَا يَكُونُ لَكَ أَن تَتَكَبَّرَ
فِيهَا فَٱخْرُجْ إِنَّكَ مِنَ ٱلصَّٰغِرِينَ ﴿١٣﴾ قَالَ أَنظِرْنِىٓ إِلَىٰ يَوْمِ يُبْعَثُونَ
﴿١٤﴾ قَالَ إِنَّكَ مِنَ ٱلْمُنظَرِينَ ﴿١٥﴾ قَالَ فَبِمَآ أَغْوَيْتَنِى لَأَقْعُدَنَّ لَهُمْ
صِرَٰطَكَ ٱلْمُسْتَقِيمَ ﴿١٦﴾ ثُمَّ لَءَاتِيَنَّهُم مِّنۢ بَيْنِ أَيْدِيهِمْ وَمِنْ خَلْفِهِمْ
وَعَنْ أَيْمَٰنِهِمْ وَعَن شَمَآئِلِهِمْ ۖ وَلَا تَجِدُ أَكْثَرَهُمْ شَٰكِرِينَ ﴿١٧﴾ قَالَ
ٱخْرُجْ مِنْهَا مَذْءُومًا مَّدْحُورًا ۖ لَّمَن تَبِعَكَ مِنْهُمْ لَأَمْلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنكُمْ
أَجْمَعِينَ ﴿١٨﴾ وَيَٰٓـَٔادَمُ ٱسْكُنْ أَنتَ وَزَوْجُكَ ٱلْجَنَّةَ فَكُلَا مِنْ حَيْثُ
شِئْتُمَا وَلَا تَقْرَبَا هَٰذِهِ ٱلشَّجَرَةَ فَتَكُونَا مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٩﴾ فَوَسْوَسَ
لَهُمَا ٱلشَّيْطَٰنُ لِيُبْدِىَ لَهُمَا مَا وُۥرِىَ عَنْهُمَا مِن سَوْءَٰتِهِمَا ۚ وَقَالَ
مَا نَهَىٰكُمَا رَبُّكُمَا عَنْ هَٰذِهِ ٱلشَّجَرَةِ إِلَّآ أَن تَكُونَا مَلَكَيْنِ
أَوْ تَكُونَا مِنَ ٱلْخَٰلِدِينَ ﴿٢٠﴾ وَقَاسَمَهُمَآ إِنِّى لَكُمَا لَمِنَ ٱلنَّٰصِحِينَ ﴿٢١﴾
فَدَلَّىٰهُمَا بِغُرُورٍ ۚ فَلَمَّا ذَاقَا ٱلشَّجَرَةَ بَدَتْ لَهُمَا سَوْءَٰتُهُمَا وَطَفِقَا
يَخْصِفَانِ عَلَيْهِمَا مِن وَرَقِ ٱلْجَنَّةِ ۖ وَنَادَىٰهُمَا رَبُّهُمَآ أَلَمْ أَنْهَكُمَا عَن
تِلْكُمَا ٱلشَّجَرَةِ وَأَقُل لَّكُمَآ إِنَّ ٱلشَّيْطَٰنَ لَكُمَا عَدُوٌّ مُّبِينٌ ﴿٢٢﴾

(12) (Allah) Ya ce: "Me ya hana ka yin sujada lokacin da Na umarce ka?" Sai ya ce: "Ai ni na fi shi alheri; Ka halicce ni da wuta, shi kuwa Ka halicce shi da tabo."

(13) Sai Ya ce: "To ka sauka daga cikinta, bai dace gare ka ka yi girman kai a cikinta ba, don haka sai ka fita, lalle kai kana cikin ƙasƙantattu."

(14) Sai ya ce: "Ka yi min jinkiri zuwa ranar da za a tashe su (mutane)."

(15) Sai Ya ce: "Lalle kai kana cikin waɗanda za a yi wa jinkiri."

(16) Ya ce: "Saboda ɓatar da ni da Ka yi, lalle sai na zaune musu tafarkinka madaidaici

(17) "Sannan lalle zan zo musu ta gabansu da kuma ta bayansu da kuma ta damansu, da kuma ta hagunsu; kuma ba za Ka samu yawancinsu masu godiya ba."

(18) Ya ce: "Ka fita daga cikinta kana abin aibatawa, korarre (daga rahama); Na rantse duk wanda ya bi ka daga cikinsu, lalle zan cika Jahannama da ku gaba ɗaya."

(19) "Kuma ya kai Adam, ka zauna cikin Aljanna, da kai da matarka, kuma ku ci duk abin da kuka ga dama, amma kada ku kusanci wannan bishiyar, sai ku kasance cikin azzalumai."

(20) Sai Shaiɗan ya yi musu waswasi, domin ya bayyana musu abin da aka ɓoye musu na tsiraicinsu, kuma ya ce: "Ba abin da ya sa Ubangijinku Ya hane ku daga wannan bishiyar, sai don kawai kada ku zama mala'iku ko kuma ku zama daga cikin dawwamammu."

(21) Kuma ya yi musu rantsuwa cewa: "Lalle ni mai yi muku nasiha ne."

(22) Sai ya yaudare su da ruɗi. Don haka yayin da suka ɗanɗani wannan bishiyar, sai tsiraicinsu ya bayyana a gare su, sai suka fara lulluɓa da ganyayen Aljanna; sai Ubangijinsu Ya kira su: "Yanzu ban hana ku cin wannan bishiyar ba, ban kuma ce da ku ba lalle Shaiɗan maƙiyi ne a gare ku mabayyani?"

قَالَا رَبَّنَا ظَلَمْنَآ أَنفُسَنَا وَإِن لَّمْ تَغْفِرْ لَنَا وَتَرْحَمْنَا لَنَكُونَنَّ
مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿٢٣﴾ قَالَ ٱهْبِطُوا۟ بَعْضُكُمْ لِبَعْضٍ عَدُوٌّ ۖ وَلَكُمْ
فِى ٱلْأَرْضِ مُسْتَقَرٌّ وَمَتَٰعٌ إِلَىٰ حِينٍ ﴿٢٤﴾ قَالَ فِيهَا تَحْيَوْنَ وَفِيهَا
تَمُوتُونَ وَمِنْهَا تُخْرَجُونَ ﴿٢٥﴾ يَٰبَنِىٓ ءَادَمَ قَدْ أَنزَلْنَا عَلَيْكُمْ
لِبَاسًا يُوَٰرِى سَوْءَٰتِكُمْ وَرِيشًا ۖ وَلِبَاسُ ٱلتَّقْوَىٰ ذَٰلِكَ خَيْرٌ ۚ
ذَٰلِكَ مِنْ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ لَعَلَّهُمْ يَذَّكَّرُونَ ﴿٢٦﴾ يَٰبَنِىٓ ءَادَمَ لَا يَفْتِنَنَّكُمُ
ٱلشَّيْطَٰنُ كَمَآ أَخْرَجَ أَبَوَيْكُم مِّنَ ٱلْجَنَّةِ يَنزِعُ عَنْهُمَا
لِبَاسَهُمَا لِيُرِيَهُمَا سَوْءَٰتِهِمَا ۗ إِنَّهُۥ يَرَىٰكُمْ هُوَ وَقَبِيلُهُۥ مِنْ
حَيْثُ لَا تَرَوْنَهُمْ ۗ إِنَّا جَعَلْنَا ٱلشَّيَٰطِينَ أَوْلِيَآءَ لِلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ
﴿٢٧﴾ وَإِذَا فَعَلُوا۟ فَٰحِشَةً قَالُوا۟ وَجَدْنَا عَلَيْهَآ ءَابَآءَنَا وَٱللَّهُ أَمَرَنَا
بِهَا ۗ قُلْ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَأْمُرُ بِٱلْفَحْشَآءِ ۖ أَتَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ
﴿٢٨﴾ قُلْ أَمَرَ رَبِّى بِٱلْقِسْطِ ۖ وَأَقِيمُوا۟ وُجُوهَكُمْ عِندَ كُلِّ مَسْجِدٍ
وَٱدْعُوهُ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ ۚ كَمَا بَدَأَكُمْ تَعُودُونَ ﴿٢٩﴾
فَرِيقًا هَدَىٰ وَفَرِيقًا حَقَّ عَلَيْهِمُ ٱلضَّلَٰلَةُ ۚ إِنَّهُمُ ٱتَّخَذُوا۟
ٱلشَّيَٰطِينَ أَوْلِيَآءَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَيَحْسَبُونَ أَنَّهُم مُّهْتَدُونَ ﴿٣٠﴾

(23) Sai suka ce: "Ya Ubangijinmu, lalle kam mun zalunci kawunanmu, kuma idan har ba Ka yi mana gafara ba, kuma ba Ka ji kan mu ba, to lalle fa za mu kasance cikin hasararru."
(24) Sai Ya ce: "Ku sauka, sashinku zai zama abokin adawa ga sashi; kuma kuna da wurin zama a ƙasa da abin jin daɗi zuwa ɗan wani lokaci."
(25) Ya ce: "A cikinta za ku rayu, kuma a cikinta za ku mutu, kuma daga cikinta za a fito da ku."
(26) Ya ku 'yan'adam, haƙiƙa Mun saukar muku da tufafi wanda zai suturce muku tsiraicinku, da kayan ado; tufafi na taƙawa kuwa wannan shi ya fi alheri. Wannan yana daga cikin ayoyin Allah, ko sa yi tuntuntuni
(27) Ya ku 'yan'adam, kada Shaiɗan ya fitine ku kamar yadda ya fitar da iyayenku daga cikin Aljanna, yana mai cire musu tufafinsu don ya nuna musu tsiraicin junansu. Lalle shi yana ganin ku, shi da jama'arsa ta inda ku ba kwa ganin su. Lalle Mu Mun sanya shaiɗanu su zamo masoya ga waɗanda ba sa yin imani
(28) Idan kuma sun aikata wani mummunan aiki sai su ce: "Mun sami iyayenmu ne a kansa, kuma Allah ne Ya umarce mu da shi." Ka ce: "Lalle Allah ba Ya umarni da mummunan aiki; yanzu kwa riƙa faɗin abin da ba ku sani ba kuna jingina wa Allah?"
(29) Ka ce: "Ubangijina Ya yi umarni da adalci; kuma ku tsai da fuskokinku (don Allah) a kowace salla, ku kuma roƙe Shi kuna masu tsantsanta addini gare Shi. Kamar yadda Ya fari halittarku, haka za ku koma (wurinsa)
(30) Wani sashi Ya shirye su, wani sashin kuma ɓata ya tabbata a kansu. Lalle su sun mayar da shaiɗanu masoya ba Allah ba, suna kuma tsammanin cewa lalle su shiryayyu ne

يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ خُذُواْ زِينَتَكُمۡ عِندَ كُلِّ مَسۡجِدٖ وَكُلُواْ وَٱشۡرَبُواْ
وَلَا تُسۡرِفُوٓاْۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلۡمُسۡرِفِينَ ٣١ قُلۡ مَنۡ حَرَّمَ زِينَةَ ٱللَّهِ
ٱلَّتِيٓ أَخۡرَجَ لِعِبَادِهِۦ وَٱلطَّيِّبَٰتِ مِنَ ٱلرِّزۡقِۚ قُلۡ هِيَ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ
فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا خَالِصَةٗ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ
لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ٣٢ قُلۡ إِنَّمَا حَرَّمَ رَبِّيَ ٱلۡفَوَٰحِشَ مَا ظَهَرَ مِنۡهَا وَمَا
بَطَنَ وَٱلۡإِثۡمَ وَٱلۡبَغۡيَ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَأَن تُشۡرِكُواْ بِٱللَّهِ مَا لَمۡ يُنَزِّلۡ
بِهِۦ سُلۡطَٰنٗا وَأَن تَقُولُواْ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٣٣ وَلِكُلِّ أُمَّةٍ
أَجَلٞۖ فَإِذَا جَآءَ أَجَلُهُمۡ لَا يَسۡتَأۡخِرُونَ سَاعَةٗ وَلَا يَسۡتَقۡدِمُونَ
٣٤ يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ إِمَّا يَأۡتِيَنَّكُمۡ رُسُلٞ مِّنكُمۡ يَقُصُّونَ عَلَيۡكُمۡ ءَايَاتِي فَمَنِ
ٱتَّقَىٰ وَأَصۡلَحَ فَلَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ٣٥ وَٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ
بِـَٔايَٰتِنَا وَٱسۡتَكۡبَرُواْ عَنۡهَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا
خَٰلِدُونَ ٣٦ فَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّنِ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوۡ كَذَّبَ
بِـَٔايَٰتِهِۦٓۚ أُوْلَٰٓئِكَ يَنَالُهُمۡ نَصِيبُهُم مِّنَ ٱلۡكِتَٰبِۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَتۡهُمۡ
رُسُلُنَا يَتَوَفَّوۡنَهُمۡ قَالُوٓاْ أَيۡنَ مَا كُنتُمۡ تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِۖ
قَالُواْ ضَلُّواْ عَنَّا وَشَهِدُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡ أَنَّهُمۡ كَانُواْ كَٰفِرِينَ ٣٧

(31) Ya ku 'yan'adam, ku yi adonku a wurin kowane masallaci(1), ku ci, kuma ku sha, amma kada ku yi almubazzaranci. Lalle Shi (Allah) ba ya son masu almubazzaranci
(32) Ka ce: "Wane ne ya haramta kayan ado na Allah wadanda (Allah) Ya fitar domin bayinsa da kuma dadadan abubuwa na arziki?" Ka ce: "Wadannan abubuwa na wadanda suka yi imani ne a nan duniya, kuma nasu ne a kebance a ranar lahira." Kamar haka ne Muke rarrabe ayoyi ga mutanen da suke da sani
(33) Ka ce, "Ubangijina kawai Ya haramta munanan ayyuka na sarari da na boye da sabo da cutar wani ba da hakki ba, kuma (Ya haramta) ku hada Allah da wani, irin abin da bai saukar da wani dalili a kai ba, kuma (Ya haramta) ku fadi wani abu game da Allah wanda ba ku sani ba.
(34) Kuma kowace al'umma tana da lokaci kayyadajje; don haka idan ajalinsu ya zo, ba za a yi musu jinkirin sa'a daya ba; ba kuma za a gaggauta musu ba
(35) Ya ku 'yan'adam, idan har manzanni suka zo muku daga cikinku, suna karanta muku ayoyina, to duk wanda ya yi takawa, kuma ya kyautata aiki, to babu jin tsoro tare da su, kuma ba za su yi bakin ciki ba
(36) Wadanda kuwa suka karyata ayoyinmu, kuma suka yi girman kai gare su, wadannan su ne ma'abota wuta; suna masu dawwama a cikinta
(37) To wa ya fi wanda ya yi wa Allah karya zalunci, ko ya karyata ayoyinsa? Wadannan rabonsu da aka rubuta a cikin littafi zai same su; har ya zuwa lokacin da manzannimu za su zo su karbi ransu, sai su ce: "Ina wadanda kuka kasance kuna kira ba Allah ba?" Sai su ce: "Sun bace mana." Kuma za su ba da shaida a kansu cewa, lalle su sun kasance kafirai

(1) Wannan ayar ta sauka ne game da mushirikai masu yin dawafi tsirara, suna cewa, wai bai dace su bauta wa Allah da tufafin da suka yi sabo da su ba.

قَالَ ٱدۡخُلُواْ فِيٓ أُمَمٖ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِكُم مِّنَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِ
فِي ٱلنَّارِۖ كُلَّمَا دَخَلَتۡ أُمَّةٞ لَّعَنَتۡ أُخۡتَهَاۖ حَتَّىٰٓ إِذَا ٱدَّارَكُواْ
فِيهَا جَمِيعٗا قَالَتۡ أُخۡرَىٰهُمۡ لِأُولَىٰهُمۡ رَبَّنَا هَٰٓؤُلَآءِ أَضَلُّونَا فَـَٔاتِهِمۡ
عَذَابٗا ضِعۡفٗا مِّنَ ٱلنَّارِۖ قَالَ لِكُلّٖ ضِعۡفٞ وَلَٰكِن لَّا تَعۡلَمُونَ
٣٨ وَقَالَتۡ أُولَىٰهُمۡ لِأُخۡرَىٰهُمۡ فَمَا كَانَ لَكُمۡ عَلَيۡنَا مِن فَضۡلٖ
فَذُوقُواْ ٱلۡعَذَابَ بِمَا كُنتُمۡ تَكۡسِبُونَ ٣٩ إِنَّ ٱلَّذِينَ
كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَٱسۡتَكۡبَرُواْ عَنۡهَا لَا تُفَتَّحُ لَهُمۡ أَبۡوَٰبُ ٱلسَّمَآءِ
وَلَا يَدۡخُلُونَ ٱلۡجَنَّةَ حَتَّىٰ يَلِجَ ٱلۡجَمَلُ فِي سَمِّ ٱلۡخِيَاطِۚ وَكَذَٰلِكَ
نَجۡزِي ٱلۡمُجۡرِمِينَ ٤٠ لَهُم مِّن جَهَنَّمَ مِهَادٞ وَمِن فَوۡقِهِمۡ غَوَاشٖۚ
وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلظَّٰلِمِينَ ٤١ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
لَا نُكَلِّفُ نَفۡسًا إِلَّا وُسۡعَهَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِۖ هُمۡ
فِيهَا خَٰلِدُونَ ٤٢ وَنَزَعۡنَا مَا فِي صُدُورِهِم مِّنۡ غِلّٖ تَجۡرِي
مِن تَحۡتِهِمُ ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ وَقَالُواْ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي هَدَىٰنَا لِهَٰذَا وَمَا كُنَّا
لِنَهۡتَدِيَ لَوۡلَآ أَنۡ هَدَىٰنَا ٱللَّهُۖ لَقَدۡ جَآءَتۡ رُسُلُ رَبِّنَا بِٱلۡحَقِّۖ
وَنُودُوٓاْ أَن تِلۡكُمُ ٱلۡجَنَّةُ أُورِثۡتُمُوهَا بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٤٣

(38) Sai Ya ce: "Ku shiga cikin jerin al'ummomin da suka shuɗe kafinku na aljannu da mutane a cikin wuta." Ko da yaushe wata al'umma ta shiga (wutar) sai ta la'anci 'yar'uwarta; har sai lokacin da suka haɗu a cikinta gaba ɗaya, sai na ƙarshensu su ce wa na farkonsu: "Ya Ubangijinmu, waɗannan ne suka ɓatar da mu, don haka Ka ninka musu azabar wuta." Sai Ya ce: "Kowanne yana da ninki, sai dai ku ba ku sani ba ne."
(39) Sai kuma na farkonsu su ce wa na ƙarshensu: "Ai ba ku da wani fifiko a kanmu; to ku ɗanɗani azaba saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa."
(40) Lalle waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu, kuma suka yi girman kai gare su, ba za a buɗe musu ƙofofin sama ba, ba kuma za su shiga Aljanna ba, har sai raƙumi ya shige ta ƙofar allura. Kuma kamar haka ne Muke saka wa masu laifi
(41) Suna da shimfiɗa a cikin Jahannama daga samansu kuma akwai wuta mai lulluɓe su. Kuma kamar haka ne Muke saka wa azzalumai
(42) Waɗanda kuwa suka yi imani, kuma suka aikata kyawawan ayyuka, ba ma ɗora wa rai, sai abin da zai iya, waɗannan su ne 'yan Aljanna, su masu dawwama ne a cikinta
(43) Muka kuma cire abin da yake cikin ƙirazansu na ƙullata, ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu; kuma za su ce: "Yabo ya tabbata ga Allah da Ya shiryar da mu ga wannan, kuma da ba za mu taɓa shiryuwa ba ba don Allah Ya shiryar da mu ba. Lalle haƙiƙa manzannin Ubangijinmu sun zo da gaskiya." Sai a kira su da cewa: "Waccan Aljannar an gadar muku da ita saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa."

وَنَادَىٰٓ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِ أَصۡحَٰبَ ٱلنَّارِ أَن قَدۡ وَجَدۡنَا مَا وَعَدَنَا
رَبُّنَا حَقّٗا فَهَلۡ وَجَدتُّم مَّا وَعَدَ رَبُّكُمۡ حَقّٗاۖ قَالُواْ نَعَمۡۚ فَأَذَّنَ
مُؤَذِّنُۢ بَيۡنَهُمۡ أَن لَّعۡنَةُ ٱللَّهِ عَلَى ٱلظَّٰلِمِينَ ٤٤ ٱلَّذِينَ يَصُدُّونَ عَن
سَبِيلِ ٱللَّهِ وَيَبۡغُونَهَا عِوَجٗا وَهُم بِٱلۡأٓخِرَةِ كَٰفِرُونَ ٤٥ وَبَيۡنَهُمَا
حِجَابٞۚ وَعَلَى ٱلۡأَعۡرَافِ رِجَالٞ يَعۡرِفُونَ كُلَّۢا بِسِيمَىٰهُمۡۚ وَنَادَوۡاْ
أَصۡحَٰبَ ٱلۡجَنَّةِ أَن سَلَٰمٌ عَلَيۡكُمۡۚ لَمۡ يَدۡخُلُوهَا وَهُمۡ يَطۡمَعُونَ ٤٦
* وَإِذَا صُرِفَتۡ أَبۡصَٰرُهُمۡ تِلۡقَآءَ أَصۡحَٰبِ ٱلنَّارِ قَالُواْ رَبَّنَا لَا تَجۡعَلۡنَا
مَعَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ٤٧ وَنَادَىٰٓ أَصۡحَٰبُ ٱلۡأَعۡرَافِ رِجَالٗا يَعۡرِفُونَهُم
بِسِيمَىٰهُمۡ قَالُواْ مَآ أَغۡنَىٰ عَنكُمۡ جَمۡعُكُمۡ وَمَا كُنتُمۡ تَسۡتَكۡبِرُونَ ٤٨
أَهَٰٓؤُلَآءِ ٱلَّذِينَ أَقۡسَمۡتُمۡ لَا يَنَالُهُمُ ٱللَّهُ بِرَحۡمَةٍۚ ٱدۡخُلُواْ ٱلۡجَنَّةَ
لَا خَوۡفٌ عَلَيۡكُمۡ وَلَآ أَنتُمۡ تَحۡزَنُونَ ٤٩ وَنَادَىٰٓ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِ أَصۡحَٰبَ
ٱلۡجَنَّةِ أَنۡ أَفِيضُواْ عَلَيۡنَا مِنَ ٱلۡمَآءِ أَوۡ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُۚ قَالُوٓاْ
إِنَّ ٱللَّهَ حَرَّمَهُمَا عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ ٥٠ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ دِينَهُمۡ لَهۡوٗا
وَلَعِبٗا وَغَرَّتۡهُمُ ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَاۚ فَٱلۡيَوۡمَ نَنسَىٰهُمۡ كَمَا نَسُواْ
لِقَآءَ يَوۡمِهِمۡ هَٰذَا وَمَا كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَجۡحَدُونَ ٥١

(44) Kuma ‘yan Aljanna za su kira ‘yan wuta cewa: “Haƙiƙa mu kam mun samu abin da Ubangijinmu Ya yi mana alƙawari gaskiya ne, shin ku ma kun sami abin da Ubangijinku Ya yi muku alƙawari gaskiya ne?” Sai su ce, “E.” Sai wani mai shela ya yi shela a tsakankaninsu cewa: “La’anar Allah ta tabbata a kan azzalumai
(45) “(Su ne) waɗanda suke hana mutane bin tafarkin Allah, kuma suke neman ya zama karkatacce, alhali su masu kafircewa ne da ranar lahira.”

(46) A tsakaninsu kuma akwai wani shamaki. Kuma a kan tozon La’arafi akwai waɗansu mazaje suna gane kowane (ɗan Aljanna da ɗan wuta) da alamominsu[1]. Kuma sai su kira ‘yan Aljanna cewa: “Amincin Allah ya tabbata a gare ku.” (Lokacin) ba su shige ta ba, amma suna kwaɗayin (shigar ta)
(47) Idan kuma an juyar da idanuwansu ɓangaren ‘yan wuta sai su ce: “Ya Ubangijinmu, kada Ka sanya mu tare da mutane azzalumai.”
(48) Sai ‘yan tozon La’arafi su kira waɗansu mazaje da suke gane su da alamominsu[2], sai su ce: “Taronku bai wadatar da ku da komai ba, da girman kan da kuka kasance kuna yi
(49) “Shin waɗannan ne waɗanda kuka rantse cewa Allah ba zai sadar da rahamarsa zuwa gare su ba?” Ku shiga Aljanna babu wani tsoro tare da ku, kuma ba za ku yi baƙin ciki ba
(50) Sai ‘yan wuta su kira ‘yan Aljanna cewa: “Ku kwararo mana ruwa ko abin da Allah Ya arzuta ku da shi.” Sai su ce: “Lalle Allah Ya haramta su ga kafirai.”
(51) (Su ne) waɗanda suka ɗauki addininsu sharholiya da wargi, kuma rayuwar duniya ta ruɗe su. To a yau za Mu manta da su, kamar yadda suka manta da saduwa da wannan yinin nasu, da kuma jayayya da suka kasance suna yi da ayoyinmu

(1) Waɗannan mazaje su ne waɗanda kyawawan ayyukansu suka yi daidai da munanansu.

(2) Su ne shugabannin mushirikai waɗanda sun san su tun a duniya, kuma a nan ma lahira sun shaida su da alamominsu na ‘yan wuta.

وَلَقَدْ جِئْنَٰهُم بِكِتَٰبٍ فَصَّلْنَٰهُ عَلَىٰ عِلْمٍ هُدًى وَرَحْمَةً
لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٥٢﴾ هَلْ يَنظُرُونَ إِلَّا تَأْوِيلَهُۥ ۚ يَوْمَ يَأْتِى تَأْوِيلُهُۥ
يَقُولُ ٱلَّذِينَ نَسُوهُ مِن قَبْلُ قَدْ جَآءَتْ رُسُلُ رَبِّنَا بِٱلْحَقِّ
فَهَل لَّنَا مِن شُفَعَآءَ فَيَشْفَعُوا۟ لَنَآ أَوْ نُرَدُّ فَنَعْمَلَ غَيْرَ ٱلَّذِى
كُنَّا نَعْمَلُ ۚ قَدْ خَسِرُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُوا۟
يَفْتَرُونَ ﴿٥٣﴾ إِنَّ رَبَّكُمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ
فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ عَلَى ٱلْعَرْشِ ۖ يُغْشِى ٱلَّيْلَ ٱلنَّهَارَ
يَطْلُبُهُۥ حَثِيثًا وَٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ وَٱلنُّجُومَ مُسَخَّرَٰتٍۭ
بِأَمْرِهِۦٓ ۗ أَلَا لَهُ ٱلْخَلْقُ وَٱلْأَمْرُ ۗ تَبَارَكَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٥٤﴾
ٱدْعُوا۟ رَبَّكُمْ تَضَرُّعًا وَخُفْيَةً ۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلْمُعْتَدِينَ ﴿٥٥﴾
وَلَا تُفْسِدُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ بَعْدَ إِصْلَٰحِهَا وَٱدْعُوهُ خَوْفًا وَطَمَعًا ۚ
إِنَّ رَحْمَتَ ٱللَّهِ قَرِيبٌ مِّنَ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٥٦﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى يُرْسِلُ
ٱلرِّيَٰحَ بُشْرًۢا بَيْنَ يَدَىْ رَحْمَتِهِۦ ۖ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَقَلَّتْ سَحَابًا ثِقَالًا
سُقْنَٰهُ لِبَلَدٍ مَّيِّتٍ فَأَنزَلْنَا بِهِ ٱلْمَآءَ فَأَخْرَجْنَا بِهِۦ مِن كُلِّ
ٱلثَّمَرَٰتِ ۚ كَذَٰلِكَ نُخْرِجُ ٱلْمَوْتَىٰ لَعَلَّكُمْ تَذَكَّرُونَ ﴿٥٧﴾

(52) Lalle haƙiƙa kuma Mun zo musu da littafin[1] da Muka bayyana shi filla-filla bisa ilimi da shiriya da rahama ga mutanen da suke yin imani
(53) Shin akwai abin da suke jira ne in ba aukuwar abin da ya labarta ba[2]?. Ranar da haƙiƙanin al'amarin zai zo, waɗanda a da suka manta da shi za su ce: "Haƙiƙa manzannin Ubangijinmu sun zo da gaskiya, shin za mu samu masu ceto da za su cece mu, ko kuma za a mayar da mu, sai mu yi aiki ba irin wanda muka kasance muna yi ba?" Haƙiƙa sun yi hasarar rayuwarsu, kuma abin da suka kasance suna ƙirƙira ya ɓace musu
(54) Lalle Ubangijinku shi ne Allah wanda Ya halicci sammai da ƙasa cikin kwanaki shida, sannan sai Ya daidaita a kan Al'arshi[3], Yana lulluɓe (duhun) dare da (hasken) yini, (kowannensu) yana neman sa (ɗan'uwansa) a gurguje, da rana da wata da taurari kuma abubuwan horewa ne da umarninsa. Haƙiƙa halitta da umarni nasa ne. Albarkatun Allah Ubangijin talikai sun yawaita
(55) Ku roƙi Ubangijinku kuna masu ƙaskantar da kai, kuma a ɓoye. Lalle Shi ba ya son masu ƙetare iyaka
(56) Kuma kada ku yi ɓarna a bayan ƙasa bayan gyara ta, kuma ku bauta masa kuna masu tsoro da kwaɗayi. Lalle rahamar Allah a kusa take da masu kyautatawa
(57) Kuma Shi ne Wanda yake aiko da iska don albishir kafin zuwan rahamarsa; har lokacin da ta ɗauko gizagizai masu nauyi (cike da ruwa), sai Mu kora shi ga wani gari matacce, sai Mu saukar da ruwa da shi, Mu kuma fitar da dukkan 'ya'yan itace a sanadiyyarsa. Kamar haka ne Muke fito da matattu don ku wa'azantu

(1) Watau Alƙur'ani mai girma.

(2) Watau zuwan ranar alƙiyama.

(3) Allah mai girma da buwaya ya daidaita a kan Al'arshi daidaiton da ya dace da girmansa.

وَٱلْبَلَدُ ٱلطَّيِّبُ يَخْرُجُ نَبَاتُهُۥ بِإِذْنِ رَبِّهِۦ ۖ وَٱلَّذِى خَبُثَ لَا يَخْرُجُ
إِلَّا نَكِدًا ۚ كَذَٰلِكَ نُصَرِّفُ ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يَشْكُرُونَ ﴿٥٨﴾
لَقَدْ أَرْسَلْنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوْمِهِۦ فَقَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مَا لَكُم
مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥٓ ۖ إِنِّىٓ أَخَافُ عَلَيْكُمْ عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿٥٩﴾
قَالَ ٱلْمَلَأُ مِن قَوْمِهِۦٓ إِنَّا لَنَرَىٰكَ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٦٠﴾ قَالَ يَٰقَوْمِ
لَيْسَ بِى ضَلَٰلَةٌ وَلَٰكِنِّى رَسُولٌ مِّن رَّبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٦١﴾
أُبَلِّغُكُمْ رِسَٰلَٰتِ رَبِّى وَأَنصَحُ لَكُمْ وَأَعْلَمُ مِنَ ٱللَّهِ
مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿٦٢﴾ أَوَعَجِبْتُمْ أَن جَآءَكُمْ ذِكْرٌ مِّن رَّبِّكُمْ
عَلَىٰ رَجُلٍ مِّنكُمْ لِيُنذِرَكُمْ وَلِتَتَّقُوا۟ وَلَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ
﴿٦٣﴾ فَكَذَّبُوهُ فَأَنجَيْنَٰهُ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥ فِى ٱلْفُلْكِ وَأَغْرَقْنَا ٱلَّذِينَ
كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا ۖ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ قَوْمًا عَمِينَ ﴿٦٤﴾ ۞ وَإِلَىٰ
عَادٍ أَخَاهُمْ هُودًا ۚ قَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ
غَيْرُهُۥٓ ۚ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿٦٥﴾ قَالَ ٱلْمَلَأُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِن قَوْمِهِۦٓ
إِنَّا لَنَرَىٰكَ فِى سَفَاهَةٍ وَإِنَّا لَنَظُنُّكَ مِنَ ٱلْكَٰذِبِينَ ﴿٦٦﴾
قَالَ يَٰقَوْمِ لَيْسَ بِى سَفَاهَةٌ وَلَٰكِنِّى رَسُولٌ مِّن رَّبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٦٧﴾

(58) Wuri kuma mai kyau, tsironsa yana fitowa (kyakkyawa) da izinin Ubangijinsa. Wuri kuwa lalatacce (shukarsa) ba ta fita sai da kyar. Kamar haka ne Muke sarrafa ayoyi ga mutanen da suke yin godiya

(59) Lalle haƙiƙa Mun aiko Nuhu zuwa ga mutanensa, sai ya ce: "Ya ku mutanena, ku bautata wa Allah, ba ku da wani abin bautawa da gaskiya sai Shi, lalle ni ina ji muku tsoron azabar wani yini mai girma."

(60) Sai manyan gari cikin mutanensa suka ce: "Lalle mu tabbas muna ganin kana cikin ɓata mabayyani."

(61) Sai ya ce: "Ya ku mutanena, babu wata ɓata tare da ni, sai dai ni Manzo ne daga Ubangijin halittu."

(62) "Ina isar muku da saƙonnin Ubangijina, ina kuma yi muku nasiha, na kuma san abin da ba ku sani ba daga Allah

(63) "Shin kun yi mamaki ne don wa'azi ya zo muku daga Ubangijinku, ta kan harshen wani mutum cikinku, don ya gargaɗe ku, don ku kuma kiyaye dokokin Allah domin a ji ƙan ku?"

(64) Sai suka ƙaryata shi, sai Muka tserar da shi da waɗanda suke tare da shi, a cikin jirgin ruwa, kuma Muka dulmiyar da waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu. Lalle su sun kasance mutane makafi

(65) Kuma Mun aika wa Adawa ɗan'uwansu Hudu. Ya ce: "Ya ku mutanena, ku bautata wa Allah, ba ku da wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. Shin ba za ku kiyaye dokokin Allah ba?"

(66) Sai manyan gari waɗanda suka kafirce cikin mutanensa suka ce: "Lalle mu tabbas muna ganin ka kana cikin wauta, kuma lalle mu tabbas muna zaton kai kana cikin maƙaryata

(67) Sai ya ce: "Ya ku mutanena, babu wata wauta a tare da ni, sai dai ni kawai Manzo ne daga Ubangijin talikai

أُبَلِّغُكُمْ رِسَٰلَٰتِ رَبِّى وَأَنَا۠ لَكُمْ نَاصِحٌ أَمِينٌ ﴿٦٨﴾ أَوَعَجِبْتُمْ أَن
جَآءَكُمْ ذِكْرٌ مِّن رَّبِّكُمْ عَلَىٰ رَجُلٍ مِّنكُمْ لِيُنذِرَكُمْ ۚ
وَٱذْكُرُوٓا۟ إِذْ جَعَلَكُمْ خُلَفَآءَ مِنۢ بَعْدِ قَوْمِ نُوحٍ وَزَادَكُمْ
فِى ٱلْخَلْقِ بَصْۜطَةً ۖ فَٱذْكُرُوٓا۟ ءَالَآءَ ٱللَّهِ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ
﴿٦٩﴾ قَالُوٓا۟ أَجِئْتَنَا لِنَعْبُدَ ٱللَّهَ وَحْدَهُۥ وَنَذَرَ مَا كَانَ يَعْبُدُ
ءَابَآؤُنَا ۖ فَأْتِنَا بِمَا تَعِدُنَآ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿٧٠﴾
قَالَ قَدْ وَقَعَ عَلَيْكُم مِّن رَّبِّكُمْ رِجْسٌ وَغَضَبٌ ۖ
أَتُجَٰدِلُونَنِى فِىٓ أَسْمَآءٍ سَمَّيْتُمُوهَآ أَنتُمْ وَءَابَآؤُكُم
مَّا نَزَّلَ ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلْطَٰنٍ ۚ فَٱنتَظِرُوٓا۟ إِنِّى مَعَكُم مِّنَ
ٱلْمُنتَظِرِينَ ﴿٧١﴾ فَأَنجَيْنَٰهُ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥ بِرَحْمَةٍ مِّنَّا
وَقَطَعْنَا دَابِرَ ٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا ۖ وَمَا كَانُوا۟ مُؤْمِنِينَ
﴿٧٢﴾ وَإِلَىٰ ثَمُودَ أَخَاهُمْ صَٰلِحًا ۚ قَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ
مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥ ۖ قَدْ جَآءَتْكُم بَيِّنَةٌ مِّن رَّبِّكُمْ ۖ
هَٰذِهِۦ نَاقَةُ ٱللَّهِ لَكُمْ ءَايَةً ۖ فَذَرُوهَا تَأْكُلْ فِىٓ أَرْضِ
ٱللَّهِ ۖ وَلَا تَمَسُّوهَا بِسُوٓءٍ فَيَأْخُذَكُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٧٣﴾

(68) "Ina isar muku da saƙonnin Ubangijina, kuma ni mai nasiha ne a gare ku, amintacce
(69) "Shin mamaki kuke yi wa'azi ya zo muku daga Ubangijinku a kan (harshen) wani mutum daga cikinku don ya gargaɗe ku? Kuma ku tuna yayin da Ya sa kuka zama masu maye gurbi bayan wucewar mutanen Nuhu, kuma Ya ƙara muku girman halitta; don haka ku tuna ni'imomin Allah, don ku rabauta."
(70) Sai suka ce: "Yanzu ka zo mana ne don mu bauta wa Allah Shi kaɗai, kuma mu ƙyale abin da iyayenmu suka kasance suna bautata wa? To ka kawo mana abin da kake yi mana alƙawarinsa(1) idan ka kasance cikin masu gaskiya."
(71) Sai ya ce: "Haƙiƙa azaba da fushi daga Ubangijinku sun faɗa a kanku. Yanzu kwa riƙa jayayya da ni a kan waɗansu sunaye da ku ne kuka ƙago su da iyayenku(2), alhalin Allah bai saukar da wata hujja a kansu ba? To ku jira (ku gani), lalle ni ma ina nan cikin masu jira tare da ku."
(72) Sai Muka tserar da shi, da waɗanda suke tare da shi da rahamarmu, Muka kuma tumɓuke tushen waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu; kuma ba su kasance muminai ba
(73) Zuwa ga Samudawa kuwa Mun aika ɗan'uwansu Salihu. Ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi; haƙiƙa hujja ta zo muku daga Ubangijinku. Wannan kuma taguwar Allah aya ce a gare ku; don haka ku ƙyale ta ta ci a bayan ƙasar Allah; kuma kar ku taɓa ta da wani mugun abu, sai wata azaba mai raɗaɗi ta shafe ku

(1) Watau azabar Allah ( ).

(2) Watau gumakan da suke bauta wa ba Allah ba.

وَٱذۡكُرُوٓاْ إِذۡ جَعَلَكُمۡ خُلَفَآءَ مِنۢ بَعۡدِ عَادٖ وَبَوَّأَكُمۡ
فِي ٱلۡأَرۡضِ تَتَّخِذُونَ مِن سُهُولِهَا قُصُورٗا وَتَنۡحِتُونَ
ٱلۡجِبَالَ بُيُوتٗاۖ فَٱذۡكُرُوٓاْ ءَالَآءَ ٱللَّهِ وَلَا تَعۡثَوۡاْ فِي
ٱلۡأَرۡضِ مُفۡسِدِينَ ٧٤ قَالَ ٱلۡمَلَأُ ٱلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُواْ مِن
قَوۡمِهِۦ لِلَّذِينَ ٱسۡتُضۡعِفُواْ لِمَنۡ ءَامَنَ مِنۡهُمۡ أَتَعۡلَمُونَ
أَنَّ صَٰلِحٗا مُّرۡسَلٞ مِّن رَّبِّهِۦۚ قَالُوٓاْ إِنَّا بِمَآ أُرۡسِلَ بِهِۦ
مُؤۡمِنُونَ ٧٥ قَالَ ٱلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُوٓاْ إِنَّا بِٱلَّذِيٓ
ءَامَنتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ ٧٦ فَعَقَرُواْ ٱلنَّاقَةَ وَعَتَوۡاْ عَنۡ
أَمۡرِ رَبِّهِمۡ وَقَالُواْ يَٰصَٰلِحُ ٱئۡتِنَا بِمَا تَعِدُنَآ إِن كُنتَ
مِنَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ٧٧ فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلرَّجۡفَةُ فَأَصۡبَحُواْ فِي دَارِهِمۡ
جَٰثِمِينَ ٧٨ فَتَوَلَّىٰ عَنۡهُمۡ وَقَالَ يَٰقَوۡمِ لَقَدۡ أَبۡلَغۡتُكُمۡ
رِسَالَةَ رَبِّي وَنَصَحۡتُ لَكُمۡ وَلَٰكِن لَّا تُحِبُّونَ ٱلنَّٰصِحِينَ
٧٩ وَلُوطًا إِذۡ قَالَ لِقَوۡمِهِۦٓ أَتَأۡتُونَ ٱلۡفَٰحِشَةَ مَا سَبَقَكُم
بِهَا مِنۡ أَحَدٖ مِّنَ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٨٠ إِنَّكُمۡ لَتَأۡتُونَ ٱلرِّجَالَ
شَهۡوَةٗ مِّن دُونِ ٱلنِّسَآءِۚ بَلۡ أَنتُمۡ قَوۡمٞ مُّسۡرِفُونَ ٨١

(74) "Kuma ku tuna lokacin da Ya sanya ku kuka zama masu maye gurbi bayan Adawa, kuma Ya zaunar da ku a bayan ƙasa, kuna yin benaye a wurarenta masu taushi, kuma kuna sassaƙa gidaje a duwatsu; don haka ku tuna ni'imomin Allah, kada kuma ku yi ɓarna a bayan ƙasa."
(75) Manyan gari waɗanda suka yi girman kai daga mutanensa, suka ce wa waɗanda suke raunana waɗanda suka yi imani daga cikinsu: "Yanzu kun san cewa Salihu Manzo ne daga wajen Ubangijinsa?" Sai suka ce; "Lalle mu dai mun yi imani da abin da aka aiko shi da shi."
(76) Waɗanda suka yi girman kai suka ce: "Lalle mu kuma mun kafirce wa abin da kuka yi imani da shi."
(77) Sai suka soke taguwar, suka kuma yi tsaurin kai game da umarnin Ubangijinsu, kuma suka ce: "Ya Salihu, ka zo mana da abin da kake mana alƙawarin zai same mu (na azaba) in ka kasance cikin manzanni."
(78) Sai wata girgizar ƙasa mai tsanani ta auka musu, sai suka wayi gari a gurfane kan gwiwoyinsu, (matattu) a cikin gidajensu
(79) Sai ya juya ya rabu da su, kuma ya ce: "Ya ku mutanena, lalle haƙiƙa na isar muku da saƙon Ubangijina, kuma na yi muku nasiha, sai dai ku ba kwa son masu nasiha."
(80) Kuma ka tuna Luɗu lokacin da ya ce wa mutanensa: "Yanzu kwa riƙa aikata mummunan aikin da babu wani mahaluƙi a duniya da ya taɓa aikata irinsa gabaninku?
(81) "Lalle ku kuna zaike wa maza don sha'awa maimakon mata. A'a, ku mutane ne maɓarnata."

وَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُوٓا۟ أَخْرِجُوهُم مِّن
قَرْيَتِكُمْ ۖ إِنَّهُمْ أُنَاسٌ يَتَطَهَّرُونَ ﴿٨٢﴾ فَأَنجَيْنَٰهُ
وَأَهْلَهُۥٓ إِلَّا ٱمْرَأَتَهُۥ كَانَتْ مِنَ ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿٨٣﴾ وَأَمْطَرْنَا
عَلَيْهِم مَّطَرًا ۖ فَٱنظُرْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُجْرِمِينَ
﴿٨٤﴾ وَإِلَىٰ مَدْيَنَ أَخَاهُمْ شُعَيْبًا ۚ قَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ
مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥ ۖ قَدْ جَآءَتْكُم بَيِّنَةٌ مِّن رَّبِّكُمْ ۖ
فَأَوْفُوا۟ ٱلْكَيْلَ وَٱلْمِيزَانَ وَلَا تَبْخَسُوا۟ ٱلنَّاسَ
أَشْيَآءَهُمْ وَلَا تُفْسِدُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ بَعْدَ إِصْلَٰحِهَا ۚ
ذَٰلِكُمْ خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٨٥﴾ وَلَا
تَقْعُدُوا۟ بِكُلِّ صِرَٰطٍ تُوعِدُونَ وَتَصُدُّونَ عَن
سَبِيلِ ٱللَّهِ مَنْ ءَامَنَ بِهِۦ وَتَبْغُونَهَا عِوَجًا ۚ وَٱذْكُرُوٓا۟
إِذْ كُنتُمْ قَلِيلًا فَكَثَّرَكُمْ ۖ وَٱنظُرُوا۟ كَيْفَ كَانَ
عَٰقِبَةُ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿٨٦﴾ وَإِن كَانَ طَآئِفَةٌ مِّنكُمْ
ءَامَنُوا۟ بِٱلَّذِىٓ أُرْسِلْتُ بِهِۦ وَطَآئِفَةٌ لَّمْ يُؤْمِنُوا۟ فَٱصْبِرُوا۟
حَتَّىٰ يَحْكُمَ ٱللَّهُ بَيْنَنَا ۚ وَهُوَ خَيْرُ ٱلْحَٰكِمِينَ ﴿٨٧﴾

(82) Ba kuwa amsar da ta fito daga bakin mutanensa sai kawai suka ce: "Ku fitar da su daga garinku; lalle su mutane ne da suke nuna su masu tsarki ne."

(83) Sai Muka tserar da shi da iyalansa, in ban da matarsa, ita ta kasance cikin waɗanda suka rage (a cikin azaba)

(84) Sai Muka yi musu ruwan azaba; to duba ka ga yaya ƙarshen masu babban laifi ya kasance?

(85) Kuma (Mun) aika wa mutanen Madyana ɗan'uwansu Shu'aibu, ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi, haƙiƙa hujja ta zo muku daga Ubangijinku; don haka ku rifa cika mudu, kuma ku (kiyaye) ma'auni, kuma kada ku tauye wa mutane abubuwansu, kuma kada ku yi ɓarna a bayan ƙasa bayan an gyara ta. Wannan shi ne mafi alheri a gare ku in kun kasance muminai

(86) "Kuma kada ku zauna a kan kowace hanya kuna tsoratar da (mutane), kuma kuna toshe hanyar Allah ga duk wanda ya yi imani da Shi, kuna kuma son ta zama karkatacciya. Kuma ku tuna (ni'imar Allah) lokacin da kuke 'yan kaɗan, sai Ya yawaita ku, kuma ku duba ku ga yaya ƙarshen maɓarnata ya kasance?

(87) "Idan kuma an sami wata ƙungiya daga cikinku sun yi imani da abin da aka aiko ni da shi, wata ƙungiyar kuma ba su yi imani ba, to ku yi haƙuri har Allah Ya yi hukunci a tsakaninmu. Kuma Shi ne Fiyayyen masu hukunci."

* قَالَ ٱلْمَلَأُ ٱلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُوا۟ مِن قَوْمِهِۦ لَنُخْرِجَنَّكَ يَٰشُعَيْبُ
وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مَعَكَ مِن قَرْيَتِنَآ أَوْ لَتَعُودُنَّ فِى مِلَّتِنَا ۚ قَالَ أَوَلَوْ
كُنَّا كَٰرِهِينَ ﴿٨٨﴾ قَدِ ٱفْتَرَيْنَا عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا إِنْ عُدْنَا فِى مِلَّتِكُم بَعْدَ
إِذْ نَجَّىٰنَا ٱللَّهُ مِنْهَا ۚ وَمَا يَكُونُ لَنَآ أَن نَّعُودَ فِيهَآ إِلَّآ أَن يَشَآءَ
ٱللَّهُ رَبُّنَا ۚ وَسِعَ رَبُّنَا كُلَّ شَىْءٍ عِلْمًا ۗ عَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلْنَا ۚ رَبَّنَا ٱفْتَحْ
بَيْنَنَا وَبَيْنَ قَوْمِنَا بِٱلْحَقِّ وَأَنتَ خَيْرُ ٱلْفَٰتِحِينَ ﴿٨٩﴾ وَقَالَ ٱلْمَلَأُ
ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِن قَوْمِهِۦ لَئِنِ ٱتَّبَعْتُمْ شُعَيْبًا إِنَّكُمْ إِذًا لَّخَٰسِرُونَ
﴿٩٠﴾ فَأَخَذَتْهُمُ ٱلرَّجْفَةُ فَأَصْبَحُوا۟ فِى دَارِهِمْ جَٰثِمِينَ ﴿٩١﴾ ٱلَّذِينَ
كَذَّبُوا۟ شُعَيْبًا كَأَن لَّمْ يَغْنَوْا۟ فِيهَا ۚ ٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ شُعَيْبًا كَانُوا۟
هُمُ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿٩٢﴾ فَتَوَلَّىٰ عَنْهُمْ وَقَالَ يَٰقَوْمِ لَقَدْ أَبْلَغْتُكُمْ
رِسَٰلَٰتِ رَبِّى وَنَصَحْتُ لَكُمْ ۖ فَكَيْفَ ءَاسَىٰ عَلَىٰ قَوْمٍ
كَٰفِرِينَ ﴿٩٣﴾ وَمَآ أَرْسَلْنَا فِى قَرْيَةٍ مِّن نَّبِىٍّ إِلَّآ أَخَذْنَآ أَهْلَهَا
بِٱلْبَأْسَآءِ وَٱلضَّرَّآءِ لَعَلَّهُمْ يَضَّرَّعُونَ ﴿٩٤﴾ ثُمَّ بَدَّلْنَا
مَكَانَ ٱلسَّيِّئَةِ ٱلْحَسَنَةَ حَتَّىٰ عَفَوا۟ وَّقَالُوا۟ قَدْ مَسَّ ءَابَآءَنَا
ٱلضَّرَّآءُ وَٱلسَّرَّآءُ فَأَخَذْنَٰهُم بَغْتَةً وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿٩٥﴾

(88) Sai manyan gari, waɗanda suka yi girman kai daga cikin mutanensa suka ce: "Lalle za mu fitar da kai, ya kai Shu'aibu, da waɗanda suka yi imani tare da kai, daga alƙaryarmu, ko kuma ku dawo cikin addininmu." (Shu'aibu) ya ce: "Ko da muna ƙin (hakan)?"

(89) "Haƙiƙa mun ƙirƙiri ƙarya, mun jingina wa Allah, in har muka komo cikin addininku, bayan kuwa Allah Ya tserar da mu daga gare shi. Kuma ba ma zai yiwu ba mu koma cikinsa sai dai idan Allah Ubangijinmu ne Ya ga dama. Kuma ilimin Ubangijinmu Ya yalwaci komai. Ga Allah kaɗai muka dogara. Ya Ubangijinmu, Ka yi hukunci tsakaninmu da mutanenmu da gaskiya, kuma Kai ne Fiyayyen masu hukunci."

(90) Sai manyan gari waɗanda suka kafirce daga cikin mutanensa, suka ce: "Wallahi idan kun bi Shu'aibu fa, lalle ku tabbas kuna cikin hasararru."

(91) Sai girgizar ƙasa ta kama su, suka wayi gari a gidajensu gurfane a kan gwiwoyinsu (matattu)

(92) Waɗanda suka ƙaryata Shu'aibu, kai ka ce ba su taɓa zama a cikinsu (gidajensu) ba, lalle waɗanda suka ƙaryata Shu'aibu sun kasance su ne hasararru

(93) Sai ya juya ya bar su, kuma ya ce: "Ya ku mutanena, lalle haƙiƙa na isar muku da saƙonnin Ubangijina, na kuma yi muku nasiha; to saboda me zan ji takaici a kan mutane kafirai?"

(94) Kuma ba Mu taɓa aiko wani annabi cikin wata alƙarya ba, (mutanensa suka ƙaryata shi) sai Mun kama su da tsananin talauci da cututtuka, ko sa ƙasƙantar da kai

(95) Sannan sai Muka musanya mahallin tsanani da jin daɗi, har dai suka yawaita, suka ce: "Haƙiƙa da can cututtuka da kuma wadata sun samu iyayenmu." Sai kawai Muka damƙe su (da azaba) ba zato ba tsammani alhalin ba sa jin (hakan zai faru)

وَلَوْ أَنَّ أَهْلَ ٱلْقُرَىٰٓ ءَامَنُوا۟ وَٱتَّقَوْا۟ لَفَتَحْنَا عَلَيْهِم بَرَكَٰتٍ
مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ وَلَٰكِن كَذَّبُوا۟ فَأَخَذْنَٰهُم بِمَا كَانُوا۟
يَكْسِبُونَ ﴿٩٦﴾ أَفَأَمِنَ أَهْلُ ٱلْقُرَىٰٓ أَن يَأْتِيَهُم بَأْسُنَا
بَيَٰتًا وَهُمْ نَآئِمُونَ ﴿٩٧﴾ أَوَأَمِنَ أَهْلُ ٱلْقُرَىٰٓ أَن يَأْتِيَهُم
بَأْسُنَا ضُحًى وَهُمْ يَلْعَبُونَ ﴿٩٨﴾ أَفَأَمِنُوا۟ مَكْرَ ٱللَّهِ ۚ
فَلَا يَأْمَنُ مَكْرَ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلْقَوْمُ ٱلْخَٰسِرُونَ ﴿٩٩﴾ أَوَلَمْ يَهْدِ
لِلَّذِينَ يَرِثُونَ ٱلْأَرْضَ مِنۢ بَعْدِ أَهْلِهَآ أَن لَّوْ نَشَآءُ
أَصَبْنَٰهُم بِذُنُوبِهِمْ ۚ وَنَطْبَعُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ فَهُمْ لَا يَسْمَعُونَ
﴿١٠٠﴾ تِلْكَ ٱلْقُرَىٰ نَقُصُّ عَلَيْكَ مِنْ أَنۢبَآئِهَا ۚ وَلَقَدْ جَآءَتْهُمْ
رُسُلُهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَمَا كَانُوا۟ لِيُؤْمِنُوا۟ بِمَا كَذَّبُوا۟ مِن
قَبْلُ ۚ كَذَٰلِكَ يَطْبَعُ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿١٠١﴾ وَمَا وَجَدْنَا
لِأَكْثَرِهِم مِّنْ عَهْدٍ ۖ وَإِن وَجَدْنَآ أَكْثَرَهُمْ لَفَٰسِقِينَ ﴿١٠٢﴾
ثُمَّ بَعَثْنَا مِنۢ بَعْدِهِم مُّوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِۦ
فَظَلَمُوا۟ بِهَا ۖ فَٱنظُرْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿١٠٣﴾
وَقَالَ مُوسَىٰ يَٰفِرْعَوْنُ إِنِّى رَسُولٌ مِّن رَّبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٠٤﴾

(96) Kuma in da a ce mutanen alƙaryu sun yi imani kuma sun tsare dokokin Allah, to lalle da Mun buɗe musu albarkatu daga sama da kuma ƙasa, sai dai sun ƙaryata, Mu kuwa sai Muka kama su da abin da suka kasance suna aikatawa

(97) Yanzu mutanen alƙaryu sun amince azabarmu ta zo musu cikin dare alhali suna bacci?

(98) Ko kuma mutanen alƙaryun sun amince azabarmu ta zo musu da hantsi suna tsakiyar wasanni?

(99) Yanzu sun amince da makarun Allah ne? To kuwa ba mai amince wa makarun Allah sai mutanen da suke asararru[1]

(100) Ko kuwa bai bayyana ba ga waɗanda suke gaje ƙasa bayan gushewar mutanenta (na farko) cewa, idan da Mun ga dama da Mun kama su da zunubansu. Kuma da Mun rufe zukatansu don haka ba za su iya ji ba?


(101) Waɗancan alƙaryun Muna ba ka labarinsu ne. Kuma lalle haƙiƙa manzanninsu sun zo musu da hujjoji bayyanannu, amma ba su kasance masu yin imani ba, saboda ƙaryatawar da suka yi a da. Kamar haka ne Allah Yake rufe zukatan kafirai

(102) Kuma yawancinsu ba Mu same su da riƙe wani alƙawari ba; haƙiƙa kuma Mun samu yawancinsu fasiƙai ne

(103) Sannan sai Muka aika Musa a bayansu da ayoyinmu, zuwa Fir'auna da manyan mutanensa, sai suka zalunci (kansu) da su; to duba ka ga, yaya ƙarshen mafarnata ya kasance?

(104)Kuma Musa ya ce: "Ya kai Fir'auna, lalle ni Manzo ne daga Ubangijin talikai

(1) A nan Allah ( ) ya ambaci makarunsa shi kaɗai bai ambaci makarun bawansa ba. To amma a cikin Suratul Anfal aya ta 30 Allah ( ) ya ambaci makarunsa da na bayinsa.


حَقِيقٌ عَلَىٰٓ أَن لَّآ أَقُولَ عَلَى ٱللَّهِ إِلَّا ٱلْحَقَّ ۚ قَدْ جِئْتُكُم بِبَيِّنَةٍ
مِّن رَّبِّكُمْ فَأَرْسِلْ مَعِىَ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿١٠٥﴾ قَالَ إِن كُنتَ
جِئْتَ بِـَٔايَةٍ فَأْتِ بِهَآ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿١٠٦﴾ فَأَلْقَىٰ
عَصَاهُ فَإِذَا هِىَ ثُعْبَانٌ مُّبِينٌ ﴿١٠٧﴾ وَنَزَعَ يَدَهُۥ فَإِذَا هِىَ بَيْضَآءُ
لِلنَّٰظِرِينَ ﴿١٠٨﴾ قَالَ ٱلْمَلَأُ مِن قَوْمِ فِرْعَوْنَ إِنَّ هَٰذَا لَسَٰحِرٌ
عَلِيمٌ ﴿١٠٩﴾ يُرِيدُ أَن يُخْرِجَكُم مِّنْ أَرْضِكُمْ ۖ فَمَاذَا تَأْمُرُونَ
﴿١١٠﴾ قَالُوٓا۟ أَرْجِهْ وَأَخَاهُ وَأَرْسِلْ فِى ٱلْمَدَآئِنِ حَٰشِرِينَ ﴿١١١﴾ يَأْتُوكَ
بِكُلِّ سَحَّارٍ عَلِيمٍ ﴿١١٢﴾ وَجَآءَ ٱلسَّحَرَةُ فِرْعَوْنَ قَالُوٓا۟ إِنَّ
لَنَا لَأَجْرًا إِن كُنَّا نَحْنُ ٱلْغَٰلِبِينَ ﴿١١٣﴾ قَالَ نَعَمْ وَإِنَّكُمْ
لَمِنَ ٱلْمُقَرَّبِينَ ﴿١١٤﴾ قَالُوا۟ يَٰمُوسَىٰٓ إِمَّآ أَن تُلْقِىَ وَإِمَّآ أَن
نَّكُونَ نَحْنُ ٱلْمُلْقِينَ ﴿١١٥﴾ قَالَ أَلْقُوا۟ ۖ فَلَمَّآ أَلْقَوْا۟ سَحَرُوٓا۟
أَعْيُنَ ٱلنَّاسِ وَٱسْتَرْهَبُوهُمْ وَجَآءُو بِسِحْرٍ عَظِيمٍ ﴿١١٦﴾
* وَأَوْحَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنْ أَلْقِ عَصَاكَ ۖ فَإِذَا هِىَ تَلْقَفُ مَا يَأْفِكُونَ
﴿١١٧﴾ فَوَقَعَ ٱلْحَقُّ وَبَطَلَ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١١٨﴾ فَغُلِبُوا۟
هُنَالِكَ وَٱنقَلَبُوا۟ صَٰغِرِينَ ﴿١١٩﴾ وَأُلْقِىَ ٱلسَّحَرَةُ سَٰجِدِينَ ﴿١٢٠﴾

(105) "Wajibi ne a kaina cewa ba zan faɗi wata magana game da Allah ba sai ta gaskiya. Haƙiƙa na zo muku da hujja bayyananniya daga Ubangijinku, don haka ka sakar min Banu Isra'ila."

(106) Sai ya ce: "Idan har kana da wata alama, to ka zo da ita, idan har kana cikin masu gaskiya.[1]"

(107) Sai ya jefar da sandarsa, sai ga shi ta zama wani irin ƙaton kumurci a fili

(108) Kuma ya zaro hannunsa, sai ga shi fari ƙal ga masu kallo

(109) Sai manyan gari daga cikin mutanen Fir'auna suka ce: "Lalle wannan tabbas mai sihiri ne, masani

(110) "Yana nufi ne ya fitar da ku daga ƙasarku, don haka me kuke yin umarni (da a yi)?"

(111) Sai suka ce: "Ka dakatar da shi da ɗan'uwansa, ka kuma tura masu yin gangami cikin birane

(112) "Za su zo maka da duk wani ƙwararren matsafi."

(113) Matsafan kuwa suka zo wa Fir'auna suka ce: "Shin tabbas muna da wani lada idan muka kasance masu rinjaye?"

(114) Ya ce, "E, kuma ma tabbas kuna cikin makusanta."

(115) Sai suka ce: "Ya kai Musa, ko dai ka (fara) jefawa, ko kuwa mu mu kasance mu ne masu (fara) jefawa."

(116) Ya ce: "Ku jefa". To yayin da suka jefa (sandunansu) sai suka sihirce idon mutane[2], kuma suka gigita su, suka zo da wani tsafi babba

(117) Muka kuma yi wahayi ga Musa cewa: "Jefa sandarka." Sai ga shi nan take tana haɗiye abin da suke ƙagowa

(118) Sai gaskiya ta tabbata, abin da kuma suka kasance suna aikatawa sai ya lalace

(119) Sai aka rinjaye su a nan, suka kuma juya a ƙasƙance

(120) Matsafa kuwa suka faɗi suna masu sujjada

(1) A al'adar annabawa ba su ne suke fara bayyana mu'ujizarsu ba, har sai an ƙalubalance su, sai Allah ( ) ya bayyana ta,don kiyaye martabar annabci kada a yi saurin ƙaryata su.

(2) Sihiri ba ya canza haƙiƙanin abu zuwa wani abu daban sai dai ya zama rufa ido kawai.

قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِرَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ﴿١٢١﴾ رَبِّ مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ﴿١٢٢﴾ قَالَ
فِرۡعَوۡنُ ءَامَنتُم بِهِۦ قَبۡلَ أَنۡ ءَاذَنَ لَكُمۡۖ إِنَّ هَٰذَا لَمَكۡرٞ
مَّكَرۡتُمُوهُ فِي ٱلۡمَدِينَةِ لِتُخۡرِجُواْ مِنۡهَآ أَهۡلَهَاۖ فَسَوۡفَ تَعۡلَمُونَ
﴿١٢٣﴾ لَأُقَطِّعَنَّ أَيۡدِيَكُمۡ وَأَرۡجُلَكُم مِّنۡ خِلَٰفٖ ثُمَّ لَأُصَلِّبَنَّكُمۡ
أَجۡمَعِينَ ﴿١٢٤﴾ قَالُوٓاْ إِنَّآ إِلَىٰ رَبِّنَا مُنقَلِبُونَ ﴿١٢٥﴾ وَمَا تَنقِمُ مِنَّآ
إِلَّآ أَنۡ ءَامَنَّا بِـَٔايَٰتِ رَبِّنَا لَمَّا جَآءَتۡنَاۚ رَبَّنَآ أَفۡرِغۡ عَلَيۡنَا صَبۡرٗا
وَتَوَفَّنَا مُسۡلِمِينَ ﴿١٢٦﴾ وَقَالَ ٱلۡمَلَأُ مِن قَوۡمِ فِرۡعَوۡنَ أَتَذَرُ مُوسَىٰ
وَقَوۡمَهُۥ لِيُفۡسِدُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَيَذَرَكَ وَـَٔالِهَتَكَۚ قَالَ سَنُقَتِّلُ
أَبۡنَآءَهُمۡ وَنَسۡتَحۡيِۦ نِسَآءَهُمۡ وَإِنَّا فَوۡقَهُمۡ قَٰهِرُونَ ﴿١٢٧﴾
قَالَ مُوسَىٰ لِقَوۡمِهِ ٱسۡتَعِينُواْ بِٱللَّهِ وَٱصۡبِرُوٓاْۖ إِنَّ ٱلۡأَرۡضَ
لِلَّهِ يُورِثُهَا مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦۖ وَٱلۡعَٰقِبَةُ لِلۡمُتَّقِينَ ﴿١٢٨﴾
قَالُوٓاْ أُوذِينَا مِن قَبۡلِ أَن تَأۡتِيَنَا وَمِنۢ بَعۡدِ مَا جِئۡتَنَاۚ قَالَ
عَسَىٰ رَبُّكُمۡ أَن يُهۡلِكَ عَدُوَّكُمۡ وَيَسۡتَخۡلِفَكُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ
فَيَنظُرَ كَيۡفَ تَعۡمَلُونَ ﴿١٢٩﴾ وَلَقَدۡ أَخَذۡنَآ ءَالَ فِرۡعَوۡنَ
بِٱلسِّنِينَ وَنَقۡصٖ مِّنَ ٱلثَّمَرَٰتِ لَعَلَّهُمۡ يَذَّكَّرُونَ ﴿١٣٠﴾

(121) Suka ce: "Mun yi imani da Ubangijin talikai
(122) "Ubangijin Musa da Haruna."
(123) Sai Fir'auna ya ce: "Yanzu kun yi imani da shi tun kafin in yi muku izini? Lalle wannan tabbas wani makirci ne da kuka ƙulla shi a nan cikin garin, don ku fitar da mutanensa daga cikinsa; to da sannu za ku sani
(124) "Lalle zan yanyanke hannayenku da ƙafafuwanku

a tarnaƙe, sannan kuma gaba ɗaya
(125) Sai suka ce: "Mu kam lalle m
(126) "Kuma ba don komai za ka azabtar da mu ba sai don kawai mun yi imani da ayoyin Ubangijinmu yayin da suka zo mana. Ya Ubangijinmu, Ka zubo mana haƙuri, kuma Ka karɓi rayukanmu muna Musulmi."
(127) Sai manyan gari cikin mutanen Fir'auna suka ce: "Yanzu za ka ƙyale Musa da mutanensa, don su yi ɓarna a bayan ƙasa, kuma ya watsar da kai da abubuwan bautarka?"[1] Sai ya ce: "Lalle za mu karkashe 'ya'yansu maza, mu ƙyale 'ya'yansu mata da rai[2], kuma lalle mu masu rinjaye ne a kansu."
(128) Sai Musa ya ce da mutanensa: "Ku nemi taimakon Allah, kuma ku yi haƙuri; lalle ƙasa mulkin Allah ce, Yana gadar da ita ga wanda Ya ga dama daga cikin bayinsa; kuma kyakkyawan ƙarshe yana tabbata ne ga masu taƙawa."
(129) Sai suka ce: "An cutar da mu tun kafin ka zo mana, da kuma bayan ka zo mana." Sai ya ce: "Ta yiwu Ubangijinku Ya halakar da abokan gabarku, kuma Ya mayar da ku halifofi a bayan ƙasa, sai Ya ga kuma, me za ku aikata?"
(130) Kuma lalle haƙiƙa Mun jarrabi iyalin gidan Fir'auna da shekaru na fari da kuma tawayar 'ya'yan itace, ko sa yi tuntuntuni

(1) Bahaushe yana cewa, ba a mugun sarki sai mugun bafade. Manyan fadawan Fir'auna ne suke zuga shi a kan ya gaggauta ɗaukar mataki a kan Musa ( ) da mabiyansa.

(2) Da alama yanzu zai riƙa kashe 'ya'yan muminai ne kaɗai. Ba kamar yadda yake kuɗin goro da farko ba ba tare da bambancewa tsakanin Banu Isra'ila waɗanda suka bi shi da waɗanda ba su bi shi ba.

فَإِذَا جَآءَتْهُمُ ٱلْحَسَنَةُ قَالُوا۟ لَنَا هَٰذِهِۦ ۖ وَإِن تُصِبْهُمْ سَيِّئَةٌ
يَطَّيَّرُوا۟ بِمُوسَىٰ وَمَن مَّعَهُۥٓ ۗ أَلَآ إِنَّمَا طَٰٓئِرُهُمْ عِندَ ٱللَّهِ
وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٣١﴾ وَقَالُوا۟ مَهْمَا تَأْتِنَا بِهِۦ
مِنْ ءَايَةٍ لِّتَسْحَرَنَا بِهَا فَمَا نَحْنُ لَكَ بِمُؤْمِنِينَ ﴿١٣٢﴾ فَأَرْسَلْنَا
عَلَيْهِمُ ٱلطُّوفَانَ وَٱلْجَرَادَ وَٱلْقُمَّلَ وَٱلضَّفَادِعَ وَٱلدَّمَ
ءَايَٰتٍ مُّفَصَّلَٰتٍ فَٱسْتَكْبَرُوا۟ وَكَانُوا۟ قَوْمًا مُّجْرِمِينَ
﴿١٣٣﴾ وَلَمَّا وَقَعَ عَلَيْهِمُ ٱلرِّجْزُ قَالُوا۟ يَٰمُوسَى ٱدْعُ لَنَا رَبَّكَ بِمَا
عَهِدَ عِندَكَ ۖ لَئِن كَشَفْتَ عَنَّا ٱلرِّجْزَ لَنُؤْمِنَنَّ لَكَ
وَلَنُرْسِلَنَّ مَعَكَ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿١٣٤﴾ فَلَمَّا كَشَفْنَا عَنْهُمُ
ٱلرِّجْزَ إِلَىٰٓ أَجَلٍ هُم بَٰلِغُوهُ إِذَا هُمْ يَنكُثُونَ ﴿١٣٥﴾ فَٱنتَقَمْنَا
مِنْهُمْ فَأَغْرَقْنَٰهُمْ فِى ٱلْيَمِّ بِأَنَّهُمْ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا وَكَانُوا۟ عَنْهَا
غَٰفِلِينَ ﴿١٣٦﴾ وَأَوْرَثْنَا ٱلْقَوْمَ ٱلَّذِينَ كَانُوا۟ يُسْتَضْعَفُونَ
مَشَٰرِقَ ٱلْأَرْضِ وَمَغَٰرِبَهَا ٱلَّتِى بَٰرَكْنَا فِيهَا ۖ وَتَمَّتْ كَلِمَتُ
رَبِّكَ ٱلْحُسْنَىٰ عَلَىٰ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ بِمَا صَبَرُوا۟ ۖ وَدَمَّرْنَا
مَا كَانَ يَصْنَعُ فِرْعَوْنُ وَقَوْمُهُۥ وَمَا كَانُوا۟ يَعْرِشُونَ ﴿١٣٧﴾

(131) Amma yayin da daddaɗan abu ya zo musu, sai su ce: "Da ma wannan namu ne." Idan kuma mummunan abu ya same su, sai su camfa Musa da waɗanda suke tare da shi. Ku saurara, kawai dai mummunan abin da ya same su daga wajen Allah yake, amma yawancinsu ba sa sanin (haka)
(132) Kuma suka ce: "Kowace irin aya ka zo mana da ita, don ka sihirce mu da ita, to fa mu ba za mu yi imani da kai ba."

(133) Sai Muka aika musu da ambaliyar ruwa da fara da ƙwarƙwata da kwaɗi da jini, a matsayin ayoyi daki-daki, sai suka yi girman kai, kuma suka kasance mutane masu babban laifi
(134) Kuma yayin da azaba ta sauka a kansu, sai suka ce: "Ya kai Musa, ka roƙa mana Ubangijinka, saboda alƙawarin da Ya yi maka; lalle idan har ka yaye mana wannan azaba, to tabbas za mu yi imani da kai, kuma za mu sakar maka Banu Isra'ila."
(135) To yayin da Muka yaye musu wannan azaba zuwa wani lokacin da za su kai gare shi, sai ga shi suna warware alƙawarin da suka yi
(136) Sai Muka azabtar da su, Muka dulmiyar da su a cikin kogi saboda sun ƙaryata ayoyinmu, kuma sun kasance gafalallu game da su
(137) Mutanen kuma da ake nuna musu fin ƙarfi a da, Muka gadar musu gabashi da yammacin ƙasar da Muka yi wa albarka; kuma kalmar Ubangijinka kyakkyawa sai ta tabbata a kan Banu Isra'ila saboda haƙurin da suka yi; kuma Muka rushe abin da Fir'auna ya kasance yana yi shi da mutanensa, da abin da suka kasance suna ginawa

وَجَٰوَزْنَا بِبَنِيٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ٱلْبَحْرَ فَأَتَوْا۟ عَلَىٰ قَوْمٍ يَعْكُفُونَ
عَلَىٰٓ أَصْنَامٍ لَّهُمْ ۚ قَالُوا۟ يَٰمُوسَى ٱجْعَل لَّنَآ إِلَٰهًا كَمَا
لَهُمْ ءَالِهَةٌ ۚ قَالَ إِنَّكُمْ قَوْمٌ تَجْهَلُونَ ﴿١٣٨﴾ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ مُتَبَّرٌ
مَّا هُمْ فِيهِ وَبَٰطِلٌ مَّا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٣٩﴾ قَالَ أَغَيْرَ ٱللَّهِ
أَبْغِيكُمْ إِلَٰهًا وَهُوَ فَضَّلَكُمْ عَلَى ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٤٠﴾ وَإِذْ أَنجَيْنَٰكُم
مِّنْ ءَالِ فِرْعَوْنَ يَسُومُونَكُمْ سُوٓءَ ٱلْعَذَابِ يُقَتِّلُونَ
أَبْنَآءَكُمْ وَيَسْتَحْيُونَ نِسَآءَكُمْ ۚ وَفِى ذَٰلِكُم بَلَآءٌ
مِّن رَّبِّكُمْ عَظِيمٌ ﴿١٤١﴾ * وَوَٰعَدْنَا مُوسَىٰ ثَلَٰثِينَ لَيْلَةً
وَأَتْمَمْنَٰهَا بِعَشْرٍ فَتَمَّ مِيقَٰتُ رَبِّهِۦٓ أَرْبَعِينَ لَيْلَةً ۚ وَقَالَ
مُوسَىٰ لِأَخِيهِ هَٰرُونَ ٱخْلُفْنِى فِى قَوْمِى وَأَصْلِحْ وَلَا تَتَّبِعْ
سَبِيلَ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿١٤٢﴾ وَلَمَّا جَآءَ مُوسَىٰ لِمِيقَٰتِنَا وَكَلَّمَهُۥ
رَبُّهُۥ ۚ قَالَ رَبِّ أَرِنِىٓ أَنظُرْ إِلَيْكَ ۚ قَالَ لَن تَرَىٰنِى وَلَٰكِنِ
ٱنظُرْ إِلَى ٱلْجَبَلِ فَإِنِ ٱسْتَقَرَّ مَكَانَهُۥ فَسَوْفَ تَرَىٰنِى ۚ فَلَمَّا
تَجَلَّىٰ رَبُّهُۥ لِلْجَبَلِ جَعَلَهُۥ دَكًّا وَخَرَّ مُوسَىٰ صَعِقًا ۚ فَلَمَّآ
أَفَاقَ قَالَ سُبْحَٰنَكَ تُبْتُ إِلَيْكَ وَأَنَا۠ أَوَّلُ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١٤٣﴾

(138) Kuma sai Muka tsallakar da Banu Isra'ila kogi, sai suka tarar da waɗansu mutane da suka dukufa a kan (bautar) gumakansu, suka ce: "Ya kai Musa, ka sa mana wani abin bauta, irin yadda waɗannan suke da abubuwan bauta." Sai ya ce: "Lalle ku mutane ne da kuke da jahilci
(139) "Lalle waɗannan abin da suke cikinsa halaka ne, kuma abin da suke aikatawa ɓarna ce."
(140) Ya ce: "Shin yanzu wani wanda ba Allah ba zan nemo muku a matsayin abin bauta, alhali Shi ne Ya fifita ku a kan sauran talikai?"
(141) Kuma ku tuna lokacin da Muka tserar da ku daga mutanen Fir'auna, (waɗanda) suke ɗandana muku mummunar azaba; suna karkashe 'ya'yanku maza, kuma suna barin 'ya'yanku mata da rai, kuma lalle a cikin wannan akwai wata jarraba babba daga Ubangijinku
(142) Mun kuma yi wa Musa alƙawarin dare talatin, muka kuma cika su da goma, sai miƙatin Ubangijinsa ya cika darare arba'in cif-cif. Sai Musa ya ce da ɗan'uwansa Haruna: "Ka wakilce ni a cikin mutanena, kuma ka daidaita (tsakaninsu), kada kuma ka bi tafarkin maɓarnata."
(143) Lokacin Kuma da Musa ya zo wajen da muka yi alƙawari da shi, Ubangijinsa kuma Ya yi magana da shi, sai ya ce: "Ya Ubangijina, nuna mini kanka in gan Ka." Sai ya ce: "Ba za ka iya gani Na ba[1], amma dubi dutsen nan, idan ya tabbata a bigirensa, to da sannu za ka gan Ni." To lokacin da Ubangijinsa Ya bayyana (da haskensa) ga dutsen, sai Ya mayar da shi rugu-rugu, sai Musa ya faɗi sumamme. To yayin da ya farfaɗo, sai ya ce: "Tsarki ya tabbata gare Ka, na tuba zuwa gare Ka, kuma ni ne farkon muminai."

(1) Muminai a nan duniya ba za su iya ganin Allah ( ) a fili ba, amma a lahira za su gan shi kamar yadda hadisai da yawa suka tabbatar.

قَالَ يَٰمُوسَىٰٓ إِنِّى ٱصْطَفَيْتُكَ عَلَى ٱلنَّاسِ بِرِسَٰلَٰتِى وَبِكَلَٰمِى
فَخُذْ مَآ ءَاتَيْتُكَ وَكُن مِّنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿١٤٤﴾ وَكَتَبْنَا
لَهُۥ فِى ٱلْأَلْوَاحِ مِن كُلِّ شَىْءٍ مَّوْعِظَةً وَتَفْصِيلًا لِّكُلِّ
شَىْءٍ فَخُذْهَا بِقُوَّةٍ وَأْمُرْ قَوْمَكَ يَأْخُذُوا۟ بِأَحْسَنِهَا سَأُو۟رِيكُمْ
دَارَ ٱلْفَٰسِقِينَ ﴿١٤٥﴾ سَأَصْرِفُ عَنْ ءَايَٰتِىَ ٱلَّذِينَ يَتَكَبَّرُونَ
فِى ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ وَإِن يَرَوْا۟ كُلَّ ءَايَةٍ لَّا يُؤْمِنُوا۟ بِهَا
وَإِن يَرَوْا۟ سَبِيلَ ٱلرُّشْدِ لَا يَتَّخِذُوهُ سَبِيلًا وَإِن يَرَوْا۟ سَبِيلَ
ٱلْغَىِّ يَتَّخِذُوهُ سَبِيلًا ۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا
وَكَانُوا۟ عَنْهَا غَٰفِلِينَ ﴿١٤٦﴾ وَٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا
وَلِقَآءِ ٱلْءَاخِرَةِ حَبِطَتْ أَعْمَٰلُهُمْ ۚ هَلْ يُجْزَوْنَ إِلَّا مَا كَانُوا۟
يَعْمَلُونَ ﴿١٤٧﴾ وَٱتَّخَذَ قَوْمُ مُوسَىٰ مِنۢ بَعْدِهِۦ مِنْ حُلِيِّهِمْ
عِجْلًا جَسَدًا لَّهُۥ خُوَارٌ ۚ أَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّهُۥ لَا يُكَلِّمُهُمْ
وَلَا يَهْدِيهِمْ سَبِيلًا ۘ ٱتَّخَذُوهُ وَكَانُوا۟ ظَٰلِمِينَ ﴿١٤٨﴾
وَلَمَّا سُقِطَ فِىٓ أَيْدِيهِمْ وَرَأَوْا۟ أَنَّهُمْ قَدْ ضَلُّوا۟ قَالُوا۟ لَئِن
لَّمْ يَرْحَمْنَا رَبُّنَا وَيَغْفِرْ لَنَا لَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿١٤٩﴾

(144) Ya ce: "Ya kai Musa, Lalle Ni na zaɓe ka a kan sauran mutane da saƙona da kuma zancena, don haka ka riƙe abin da na ba ka, kuma ka kasance cikin masu godiya."
(145) Mun kuma rubuta masa komai a cikin allunan (Attaura) don wa'azi da bayani filla-filla na kowane irin abu, don haka ka riƙe su da kyau, kuma ka umarci mutanenka su yi riƙo da mafi kyawun abin da yake cikinsu. Da sannu zan nuna muku gidajen fasiƙai[1]."
(146) Zan kautar da waɗanda suke yin girman kai a bayan ƙasa ba tare da haƙƙi ba daga (fahimtar) ayoyina; idan kuma za su ga kowace irin aya ba za su yi imani da ita ba, idan kuma da za su ga hanyar shiriya ba za su riƙe ta hanyar bi ba, (amma) idan kuwa za su ga hanyar ɓata, to za su riƙe ta hanyar bi. Wannan kuwa saboda sun ƙaryata ayoyinmu, kuma sun kasance gafalallu ga barin su
(147) Waɗanda kuma suka ƙaryata ayoyinmu da haɗuwa a ranar alƙiyama, ayyukansu sun rushe. Shin kuwa za a yi musu wani sakamako ne in ba abin da suka kasance suna aikatawa ba?
(148) Mutanen Musa kuma a bayansa sun ƙera wani ɗan maraƙi daga kayan adonsu mai surar jiki yana wata ƙara (don su bauta masa). Shin ba su ga cewa ba ya yi musu Magana, kuma ba ya iya shiryar da su wani tafarki? Sun riƙe shi (a matsayin abin bauta), kuma sun tabbata azzalumai
(149) Kuma lokacin da suka yi nadama, suka gane cewa sun ɓata, sai suka ce: "Matuƙar Ubangijinmu bai ji ƙan mu ba, kuma bai gafarta mana ba, lalle za mu kasance cikin hasararru."

(1) Wasu sun ce ana nufin wutar Jahannama. Wasu kuma sun ce, ana nufin Baitul Maƙdis, saboda mazaunanta a wannan lokaci mushirikai ne. Wasu kuma sun ce, ana nufin ƙasar Masar da Baitul Maƙdisi baki ɗaya.

وَلَمَّا رَجَعَ مُوسَىٰٓ إِلَىٰ قَوْمِهِۦ غَضْبَٰنَ أَسِفًا قَالَ بِئْسَمَا خَلَفْتُمُونِى
مِنۢ بَعْدِىٓ ۖ أَعَجِلْتُمْ أَمْرَ رَبِّكُمْ ۖ وَأَلْقَى ٱلْأَلْوَاحَ وَأَخَذَ بِرَأْسِ
أَخِيهِ يَجُرُّهُۥٓ إِلَيْهِ ۚ قَالَ ٱبْنَ أُمَّ إِنَّ ٱلْقَوْمَ ٱسْتَضْعَفُونِى وَكَادُوا۟
يَقْتُلُونَنِى فَلَا تُشْمِتْ بِىَ ٱلْأَعْدَآءَ وَلَا تَجْعَلْنِى مَعَ ٱلْقَوْمِ
ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٥٠﴾ قَالَ رَبِّ ٱغْفِرْ لِى وَلِأَخِى وَأَدْخِلْنَا فِى رَحْمَتِكَ ۖ
وَأَنتَ أَرْحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ ﴿١٥١﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُوا۟ ٱلْعِجْلَ سَيَنَالُهُمْ
غَضَبٌ مِّن رَّبِّهِمْ وَذِلَّةٌ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۚ وَكَذَٰلِكَ نَجْزِى
ٱلْمُفْتَرِينَ ﴿١٥٢﴾ وَٱلَّذِينَ عَمِلُوا۟ ٱلسَّيِّـَٔاتِ ثُمَّ تَابُوا۟ مِنۢ
بَعْدِهَا وَءَامَنُوٓا۟ إِنَّ رَبَّكَ مِنۢ بَعْدِهَا لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٥٣﴾
وَلَمَّا سَكَتَ عَن مُّوسَى ٱلْغَضَبُ أَخَذَ ٱلْأَلْوَاحَ ۖ وَفِى نُسْخَتِهَا
هُدًى وَرَحْمَةٌ لِّلَّذِينَ هُمْ لِرَبِّهِمْ يَرْهَبُونَ ﴿١٥٤﴾ وَٱخْتَارَ مُوسَىٰ
قَوْمَهُۥ سَبْعِينَ رَجُلًا لِّمِيقَٰتِنَا ۖ فَلَمَّآ أَخَذَتْهُمُ ٱلرَّجْفَةُ قَالَ
رَبِّ لَوْ شِئْتَ أَهْلَكْتَهُم مِّن قَبْلُ وَإِيَّىَّ ۖ أَتُهْلِكُنَا بِمَا فَعَلَ
ٱلسُّفَهَآءُ مِنَّا ۖ إِنْ هِىَ إِلَّا فِتْنَتُكَ تُضِلُّ بِهَا مَن تَشَآءُ وَتَهْدِى
مَن تَشَآءُ ۖ أَنتَ وَلِيُّنَا فَٱغْفِرْ لَنَا وَٱرْحَمْنَا ۖ وَأَنتَ خَيْرُ ٱلْغَٰفِرِينَ ﴿١٥٥﴾

(150) Lokacin kuma da Musa ya dawo wajen mutanensa a fusace yana mai damuwa, sai ya ce: "Tir da abin da kuka aikata bayana. Yanzu kwa gaggauto al'amarin Ubangijinku?" Sai ya jefar da allunan, ya kama kan ɗan'uwansa yana jan sa zuwa gare shi. Sai (Haruna) ya ce: "Ya kai ɗan'ummata, mutanen nan haƙiƙa sun raina ni, har ma sun kusa kashe ni, don haka kar ka sa maƙiya su yi min dariya, kuma kada ka sa ni cikin mutane azzalumai."
(151) Sai ya ce: "Ya Ubangijina, Ka gafarta mini ni da ɗan'uwana, kuma Ka shigar da mu cikin rahamarka; kuma Kai ne Fiyayyen masu jin ƙai."
(152) Lalle waɗannan da suka riƙi ɗan maraƙi (abin bauta) fushin Ubangijinsu zai same su da ƙasƙanci a cikin rayuwar duniya. Kuma kamar haka ne Muke saka wa masu ƙage
(153) Waɗanda kuma suka aikata munanan ayyuka, sannan suka tuba daga baya, kuma suka yi imani, lalle Ubangijinka bayansa (tuban), tabbas Mai gafara ne, Mai jin ƙai
(154) Yayin kuma da Musa ya huce, sai ya ɗauki allunan nan (na Attaura); kuma abin da aka rubuta a cikinsu shiriya ne da rahama ga waɗanda suke tsoron Ubangijinsu
(155) Musa kuma ya zaɓi mutanensa, maza (na musamman) su saba'in don alƙawarinmu[1]; to yayin da wata tsawa ta kama su, sai ya ce: "Ya Ubangijina, idan da Ka ga dama da tun tuni Ka hallakar da su har da ni kaina. Yanzu Ka halaka mu saboda abin da wasu wawaye daga cikinmu suka aikata? Lalle wannan ba komai ba ne face jarrabawa daga gare Ka, Kana ɓatar da wanda Ka ga dama; Kana kuma shiryar da wanda Ka ga dama; Kai ne Majiɓincin lamarinmu, don haka Ka gafarta mana, kuma Ka ji ƙan mu, kuma Kai ne Fiyayyen masu gafara

(1) Watau ganawa da Allah don su gabatar da uzurinsu game da bautar ɗan maraƙi da suka yi, su wakilci 'yan'uwansu wajen neman gafarar Allah.

* وَٱكۡتُبۡ لَنَا فِي هَٰذِهِ ٱلدُّنۡيَا حَسَنَةٗ وَفِي ٱلۡأٓخِرَةِ
إِنَّا هُدۡنَآ إِلَيۡكَۚ قَالَ عَذَابِيٓ أُصِيبُ بِهِۦ مَنۡ أَشَآءُۖ وَرَحۡمَتِي
وَسِعَتۡ كُلَّ شَيۡءٖۚ فَسَأَكۡتُبُهَا لِلَّذِينَ يَتَّقُونَ وَيُؤۡتُونَ
ٱلزَّكَوٰةَ وَٱلَّذِينَ هُم بِـَٔايَٰتِنَا يُؤۡمِنُونَ ١٥٦ ٱلَّذِينَ يَتَّبِعُونَ
ٱلرَّسُولَ ٱلنَّبِيَّ ٱلۡأُمِّيَّ ٱلَّذِي يَجِدُونَهُۥ مَكۡتُوبًا عِندَهُمۡ
فِي ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَٱلۡإِنجِيلِ يَأۡمُرُهُم بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَىٰهُمۡ
عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَيُحِلُّ لَهُمُ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَيُحَرِّمُ عَلَيۡهِمُ
ٱلۡخَبَٰٓئِثَ وَيَضَعُ عَنۡهُمۡ إِصۡرَهُمۡ وَٱلۡأَغۡلَٰلَ ٱلَّتِي كَانَتۡ
عَلَيۡهِمۡۚ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِهِۦ وَعَزَّرُوهُ وَنَصَرُوهُ وَٱتَّبَعُواْ
ٱلنُّورَ ٱلَّذِيٓ أُنزِلَ مَعَهُۥٓ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ١٥٧
قُلۡ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنِّي رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيۡكُمۡ جَمِيعًا ٱلَّذِي
لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ يُحۡيِۦ وَيُمِيتُۖ
فَـَٔامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِ ٱلنَّبِيِّ ٱلۡأُمِّيِّ ٱلَّذِي يُؤۡمِنُ بِٱللَّهِ
وَكَلِمَٰتِهِۦ وَٱتَّبِعُوهُ لَعَلَّكُمۡ تَهۡتَدُونَ ١٥٨ وَمِن
قَوۡمِ مُوسَىٰٓ أُمَّةٞ يَهۡدُونَ بِٱلۡحَقِّ وَبِهِۦ يَعۡدِلُونَ ١٥٩

(156) "Kuma Ka rubuta mana kyakkyawan abu a cikin wannan duniyar, haka ma a lahira, lalle mu mun tuba zuwa gare Ka." (Allah) Ya ce: "Ina saukar da azabata a kan wanda Na ga dama; rahamata kuwa ta yalwaci komai. Don haka da sannu zan rubuta ta ga waɗanda suke kiyaye dokokin Allah, kuma suke bayar da zakka da kuma waɗanda suke yin imani da ayoyinmu

(157) "(Su ne) waɗanda suke bin Manzo Annabi Ummiyyi, wanda suke samun sa a rubuce a wurinsu a cikin Attaura da Linjila, yana umartar su da kyakkyawan abu, kuma yana hana su mummuna, kuma yana halatta musu daɗaɗan abubuwa, yana kuma haramta musu ƙazantattu, kuma yana sauke musu nauyaye-nauyayensu da ƙuƙumce-ƙuƙumcen da suka kasance a kansu(1). Don haka waɗanda suka yi imani da shi, kuma suka ƙarfafe shi, suka kuma taimake shi, suka bi hasken da aka saukar tare da shi, waɗannan su ne masu rabauta."

(158) Ka ce: "Ya ku mutane, lalle ni Manzon Allah ne zuwa gare ku gaba ɗaya, wanda Yake da mallakar sammai da ƙasa, babu abin bauta wa da gaskiya sai Shi; Shi ne Yake rayawa, kuma Shi Yake kashewa; don haka ku yi imani da Allah da Manzonsa Annabi Ummiyyi, wanda yake yin imani da Allah da kalmominsa, kuma ku bi shi don ku zama shiryayyu."

(159) Kuma daga cikin mutanen Musa akwai wata jama'a waɗanda suke shiryarwa da gaskiya, da kuma ita ne suke yin hukunci na adalci(2)

(1) Nauyaye-nauyayensu su ne abubuwa masu wuya da aka wajabta musu aiki da su a littafin Attaura. Ƙuƙumce-ƙuƙumcensu kuwa su ne abubuwan da aka tsananta musu haramcinsu masu kama da ƙuƙumi.

(2) Su ne waɗanda suka yi Imani da Annabi Muhammadu ( ).

وَقَطَّعْنَٰهُمُ ٱثْنَتَىْ عَشْرَةَ أَسْبَاطًا أُمَمًا ۚ وَأَوْحَيْنَآ إِلَىٰ
مُوسَىٰٓ إِذِ ٱسْتَسْقَىٰهُ قَوْمُهُۥٓ أَنِ ٱضْرِب بِّعَصَاكَ ٱلْحَجَرَ ۖ
فَٱنۢبَجَسَتْ مِنْهُ ٱثْنَتَا عَشْرَةَ عَيْنًا ۖ قَدْ عَلِمَ كُلُّ أُنَاسٍ
مَّشْرَبَهُمْ ۚ وَظَلَّلْنَا عَلَيْهِمُ ٱلْغَمَٰمَ وَأَنزَلْنَا عَلَيْهِمُ
ٱلْمَنَّ وَٱلسَّلْوَىٰ ۖ كُلُوا۟ مِن طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقْنَٰكُمْ ۚ وَمَا
ظَلَمُونَا وَلَٰكِن كَانُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿١٦٠﴾
وَإِذْ قِيلَ لَهُمُ ٱسْكُنُوا۟ هَٰذِهِ ٱلْقَرْيَةَ وَكُلُوا۟ مِنْهَا
حَيْثُ شِئْتُمْ وَقُولُوا۟ حِطَّةٌ وَٱدْخُلُوا۟ ٱلْبَابَ سُجَّدًا
نَّغْفِرْ لَكُمْ خَطِيٓـَٰتِكُمْ ۚ سَنَزِيدُ ٱلْمُحْسِنِينَ
﴿١٦١﴾ فَبَدَّلَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ مِنْهُمْ قَوْلًا غَيْرَ ٱلَّذِى قِيلَ
لَهُمْ فَأَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ رِجْزًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ بِمَا كَانُوا۟
يَظْلِمُونَ ﴿١٦٢﴾ وَسْـَٔلْهُمْ عَنِ ٱلْقَرْيَةِ ٱلَّتِى كَانَتْ
حَاضِرَةَ ٱلْبَحْرِ ۘ إِذْ يَعْدُونَ فِى ٱلسَّبْتِ إِذْ تَأْتِيهِمْ
حِيتَانُهُمْ يَوْمَ سَبْتِهِمْ شُرَّعًا وَيَوْمَ لَا يَسْبِتُونَ ۙ لَا تَأْتِيهِمْ ۚ
كَذَٰلِكَ نَبْلُوهُم بِمَا كَانُوا۟ يَفْسُقُونَ ﴿١٦٣﴾

(160) Mun kuma karkasa su ƙabilu goma sha biyu daban-daban[1], sai Muka kuma yi wahayi ga Musa yayin da mutanensa suka nemi ya shayar da su ruwa cewa: "Ka doki dutse da sandarka," sai idanun ruwa goma sha biyu suka ɓuɓɓugo daga jikinsa. Haƙiƙa kowace ƙabila ta san mashayarta. Muka kuma yi musu inuwa da girgije, kuma Muka saukar musu da darɓa da tsuntsayen salwa; (muka ce:) "Ku ci daga daddaɗan abin da Muka arzurta ku da shi." Kuma ba su zalunce Mu ba, sai dai kansu suka kasance suna zalunta

(161) Kuma ka tuna lokacin da aka ce musu: "Ku zauna a wannan alƙarya, kuma ku ci daga gare ta a duk inda kuka ga dama, ku kuma ce: Hiɗɗa (wato Allah Ka share mana laifukanmu), ku kuma shiga ta ƙofar alƙaryar kuna masu sujjada, za Mu gafarta muku zunubanku, kuma za Mu ƙara wa masu kyautatawa."

(162) Sai waɗanda suka yi zalunci a cikinsu suka canja magana daban da wadda aka faɗa musu, sai Muka aiko musu da wata azaba daga sama, saboda abin da suka kasance suna yi na zalunci

(163) Kuma ka tambaye su game da (mutanen) alƙaryar nan wadda take dab da gaɓar teku, yayin da suke ƙetare iyaka a ranar Asabar, yayin da kifayensu suke zuwa a ranar Asabar baja-baja, amma ranar da ba Asabar ba kuwa ba sa zuwa. Kamar haka ne muka jarrabe su saboda abin da suka kasance suna yi na fasiƙanci

(1) Su ne zuriyyar 'ya'yan Annabi Ya'aƙub ( ) goma sha biyu.

وَإِذْ قَالَتْ أُمَّةٌ مِّنْهُمْ لِمَ تَعِظُونَ قَوْمًا ۙ اللَّهُ مُهْلِكُهُمْ أَوْ مُعَذِّبُهُمْ
عَذَابًا شَدِيدًا ۖ قَالُوا مَعْذِرَةً إِلَىٰ رَبِّكُمْ وَلَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ ﴿١٦٤﴾
فَلَمَّا نَسُوا مَا ذُكِّرُوا بِهِ أَنجَيْنَا الَّذِينَ يَنْهَوْنَ عَنِ السُّوءِ
وَأَخَذْنَا الَّذِينَ ظَلَمُوا بِعَذَابٍ بَئِيسٍ بِمَا كَانُوا يَفْسُقُونَ ﴿١٦٥﴾
فَلَمَّا عَتَوْا عَن مَّا نُهُوا عَنْهُ قُلْنَا لَهُمْ كُونُوا قِرَدَةً خَاسِئِينَ ﴿١٦٦﴾
وَإِذْ تَأَذَّنَ رَبُّكَ لَيَبْعَثَنَّ عَلَيْهِمْ إِلَىٰ يَوْمِ الْقِيَامَةِ مَن يَسُومُهُمْ
سُوءَ الْعَذَابِ ۗ إِنَّ رَبَّكَ لَسَرِيعُ الْعِقَابِ وَإِنَّهُ لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ
﴿١٦٧﴾ وَقَطَّعْنَاهُمْ فِي الْأَرْضِ أُمَمًا ۖ مِّنْهُمُ الصَّالِحُونَ وَمِنْهُمْ
دُونَ ذَٰلِكَ ۖ وَبَلَوْنَاهُم بِالْحَسَنَاتِ وَالسَّيِّئَاتِ لَعَلَّهُمْ
يَرْجِعُونَ ﴿١٦٨﴾ فَخَلَفَ مِن بَعْدِهِمْ خَلْفٌ وَرِثُوا الْكِتَابَ
يَأْخُذُونَ عَرَضَ هَٰذَا الْأَدْنَىٰ وَيَقُولُونَ سَيُغْفَرُ لَنَا وَإِن
يَأْتِهِمْ عَرَضٌ مِّثْلُهُ يَأْخُذُوهُ ۚ أَلَمْ يُؤْخَذْ عَلَيْهِم مِّيثَاقُ الْكِتَابِ
أَن لَّا يَقُولُوا عَلَى اللَّهِ إِلَّا الْحَقَّ وَدَرَسُوا مَا فِيهِ ۗ وَالدَّارُ الْآخِرَةُ
خَيْرٌ لِّلَّذِينَ يَتَّقُونَ ۖ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿١٦٩﴾ وَالَّذِينَ يُمَسِّكُونَ
بِالْكِتَابِ وَأَقَامُوا الصَّلَاةَ إِنَّا لَا نُضِيعُ أَجْرَ الْمُصْلِحِينَ ﴿١٧٠﴾

(164) Kuma ka tuna lokacin da wata jama'a cikinsu suka ce: "Don me za ku rika wa'azi ga wadansu mutanen da idan Allah Ya ga dama sai Ya hallakar da su ko Ya yi musu azaba mai tsanani?" Sai suka ce: "Don yanke hanzari ne a wurin Ubangijinku ko watakila kuma sa kiyaye dokokin Allah."

(165) To yayin da suka yi watsi da abin da aka yi musu wa'azi da shi, sai Muka tserar da wadanda suke hana mummunan aiki, Muka kuma kama wadanda suka yi zalunci, da wata mummunar azaba, saboda abin da suka rika yi na fasikanci

(166) To yayin da suka yi tsaurin kai a kan abin da aka hana su, sai Muka ce da su: "Ku zama birrai, kaskantattu."

(167) Kuma ka tuna lokacin da Ubangijinka Ya yi shela, lalle zai aiko musu da wanda zai dandana musu mummunar azaba, har ya zuwa ranar tashin alkiyama. Lalle Ubangijinka Mai gaggawar ukuba ne, kuma lalle shi tabbas Mai gafara ne, Mai jin kai

(168) Kuma Mun rarraba su kabilu daban-daban a bayan kasa; a cikinsu akwai salihai, kuma daga cikinsu akwai koma bayan haka; kuma Mun jarrabe su da kyawawan abubuwa da munana, don su komo (zuwa hanya)

(169) Sai wadansu bara-gurbi suka maye bayansu, sun gaji littafin (Attaura), suna karbar abin duniya, suna kuma cewa: "Za a gafarta mana." Kuma idan wani abin duniyar irinsa ya zo musu sai su sake karbar sa. Shin yanzu ba a dauki alkawari daga wurinsu ba a cikin littafin (Attaura) cewa, kada su fadi wata magana game da Allah sai gaskiya, kuma sun karanta abin da yake cikinsa? Kuma lalle gidan lahira shi ne mafi alheri ga dukkan wadanda suke da takawa. Shin ba za ku hankalta ba?

(170) Wadanda kuwa suke riko da Littafi, kuma suke tsayar da salla, to lalle Mu ba ma tozarta ladan masu gyara

وَإِذْ نَتَقْنَا ٱلْجَبَلَ فَوْقَهُمْ كَأَنَّهُۥ ظُلَّةٌ وَظَنُّوٓا۟ أَنَّهُۥ وَاقِعٌۢ بِهِمْ
خُذُوا۟ مَآ ءَاتَيْنَٰكُم بِقُوَّةٍ وَٱذْكُرُوا۟ مَا فِيهِ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿١٧١﴾
وَإِذْ أَخَذَ رَبُّكَ مِنۢ بَنِىٓ ءَادَمَ مِن ظُهُورِهِمْ ذُرِّيَّتَهُمْ وَأَشْهَدَهُمْ
عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ أَلَسْتُ بِرَبِّكُمْ ۖ قَالُوا۟ بَلَىٰ شَهِدْنَآ ۛ أَن تَقُولُوا۟ يَوْمَ
ٱلْقِيَٰمَةِ إِنَّا كُنَّا عَنْ هَٰذَا غَٰفِلِينَ ﴿١٧٢﴾ أَوْ تَقُولُوٓا۟ إِنَّمَآ أَشْرَكَ
ءَابَآؤُنَا مِن قَبْلُ وَكُنَّا ذُرِّيَّةً مِّنۢ بَعْدِهِمْ ۖ أَفَتُهْلِكُنَا
بِمَا فَعَلَ ٱلْمُبْطِلُونَ ﴿١٧٣﴾ وَكَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلْءَايَٰتِ وَلَعَلَّهُمْ
يَرْجِعُونَ ﴿١٧٤﴾ وَٱتْلُ عَلَيْهِمْ نَبَأَ ٱلَّذِىٓ ءَاتَيْنَٰهُ ءَايَٰتِنَا فَٱنسَلَخَ
مِنْهَا فَأَتْبَعَهُ ٱلشَّيْطَٰنُ فَكَانَ مِنَ ٱلْغَاوِينَ ﴿١٧٥﴾ وَلَوْ شِئْنَا
لَرَفَعْنَٰهُ بِهَا وَلَٰكِنَّهُۥٓ أَخْلَدَ إِلَى ٱلْأَرْضِ وَٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ ۚ فَمَثَلُهُۥ
كَمَثَلِ ٱلْكَلْبِ إِن تَحْمِلْ عَلَيْهِ يَلْهَث أَوْ تَتْرُكْهُ
يَلْهَث ذَّٰلِكَ مَثَلُ ٱلْقَوْمِ ٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا ۚ فَٱقْصُصِ
ٱلْقَصَصَ لَعَلَّهُمْ يَتَفَكَّرُونَ ﴿١٧٦﴾ سَآءَ مَثَلًا ٱلْقَوْمُ ٱلَّذِينَ
كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا وَأَنفُسَهُمْ كَانُوا۟ يَظْلِمُونَ ﴿١٧٧﴾ مَن يَهْدِ ٱللَّهُ
فَهُوَ ٱلْمُهْتَدِ ۖ وَمَن يُضْلِلْ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْخَٰسِرُونَ ﴿١٧٨﴾

(171) Ka tuna kuma lokacin da Muka ɗaga dutse a samansu kamar girgije, kuma suka sakankance cewa zai rikito musu, (Muka ce da su): "Ku riƙe abin da Muka ba ku da kyau, kuma ku tuna abin da yake cikinsa, don su zamo masu kiyaye dokokin Allah."
(172) Ka tuna kuma lokacin da Ubangijinka Ya fitar da zurriyar 'yan'adam daga tsatsonsu[1], Y
a kuma sa su suka yi wa kansu shaida, (Ya ce da su): "Yanzu ba Ni ne Ubangijinku ba?" Suka ce: "E Kai ne, mun shaida." Don kada a ranar alƙiyama ku ce: "Lalle mu mun kasance gafalallu a kan wannan."
(173) Ko kuma ku ce: "Iyayenmu da suka gabace mu kawai suka yi shirka, mu kuma zurriya ce da muka kasance a bayansu; yanzu Ka hallakar da mu saboda abin da maɓarnata suka yi?"
(174) Kuma kamar haka ne Muke bayyana ayoyi, don su komo wa (gaskiya)
(175) Ka kuma karanta musu labarin wannan da Muka ba shi ayoyinmu, sai ya saluɓe (jikinsa) daga gare su, sai Shaiɗan ya bi shi, don haka ya kasance cikin halakakku
(176) Kuma da Mun ga dama da Mun ɗaukaka shi a sanadiyyarsu, amma kuma shi ya karkata zuwa ga duniya, don haka ya biye wa son zuciyarsa. To misalinsa kamar misalin kare ne, idan ka kai masa ɗauki ya yi lallage, idan ma ka ƙyale shi zai yi lallage, wannan shi ne misalin waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu. Don haka ka ba da labari don su yi tunani
(177) Misalin waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu ya munana, kuma kawunansu suka kasance suna zalunta
(178) Wanda Allah Ya shiryar, to wannan shi ne shiryayye; wanda kuwa Ya ɓatar, to waɗannan su ne hasararru

(1) Bayan Allah ( ) ya halicci Adamu ( ) sai ya shafa bayansa sai duk wani rai da Allah zai halicce shi daga cikin zuriyyarsa ha zuwa tashin ƙiyama ya fito daga tsatsonsa.

وَلَقَدْ ذَرَأْنَا لِجَهَنَّمَ كَثِيرًا مِّنَ ٱلْجِنِّ وَٱلْإِنسِ ۖ لَهُمْ قُلُوبٌ لَّا يَفْقَهُونَ
بِهَا وَلَهُمْ أَعْيُنٌ لَّا يُبْصِرُونَ بِهَا وَلَهُمْ ءَاذَانٌ لَّا يَسْمَعُونَ بِهَآ ۚ
أُو۟لَٰٓئِكَ كَٱلْأَنْعَٰمِ بَلْ هُمْ أَضَلُّ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْغَٰفِلُونَ ﴿١٧٩﴾ وَلِلَّهِ
ٱلْأَسْمَآءُ ٱلْحُسْنَىٰ فَٱدْعُوهُ بِهَا ۖ وَذَرُوا۟ ٱلَّذِينَ يُلْحِدُونَ فِىٓ أَسْمَٰٓئِهِۦ ۚ
سَيُجْزَوْنَ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٨٠﴾ وَمِمَّنْ خَلَقْنَآ أُمَّةٌ يَهْدُونَ بِٱلْحَقِّ
وَبِهِۦ يَعْدِلُونَ ﴿١٨١﴾ وَٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا سَنَسْتَدْرِجُهُم
مِّنْ حَيْثُ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٨٢﴾ وَأُمْلِى لَهُمْ ۚ إِنَّ كَيْدِى مَتِينٌ ﴿١٨٣﴾ أَوَلَمْ
يَتَفَكَّرُوا۟ ۗ مَا بِصَاحِبِهِم مِّن جِنَّةٍ ۚ إِنْ هُوَ إِلَّا نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿١٨٤﴾
أَوَلَمْ يَنظُرُوا۟ فِى مَلَكُوتِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا خَلَقَ ٱللَّهُ
مِن شَىْءٍ وَأَنْ عَسَىٰٓ أَن يَكُونَ قَدِ ٱقْتَرَبَ أَجَلُهُمْ ۖ فَبِأَىِّ حَدِيثٍ
بَعْدَهُۥ يُؤْمِنُونَ ﴿١٨٥﴾ مَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَلَا هَادِىَ لَهُۥ ۚ وَيَذَرُهُمْ
فِى طُغْيَٰنِهِمْ يَعْمَهُونَ ﴿١٨٦﴾ يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلسَّاعَةِ أَيَّانَ مُرْسَىٰهَا ۖ
قُلْ إِنَّمَا عِلْمُهَا عِندَ رَبِّى ۖ لَا يُجَلِّيهَا لِوَقْتِهَآ إِلَّا هُوَ ۚ ثَقُلَتْ فِى
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ لَا تَأْتِيكُمْ إِلَّا بَغْتَةً ۗ يَسْـَٔلُونَكَ كَأَنَّكَ حَفِىٌّ عَنْهَا ۖ
قُلْ إِنَّمَا عِلْمُهَا عِندَ ٱللَّهِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٨٧﴾

(179) Kuma lalle haƙiƙa Mun halitta wa Jahannama da yawa daga cikin aljannu da mutane; ga su da zukata da ba sa hankalta da su, ga kuma idanu da ba sa kallo da su, ga kunnuwa da ba sa sauraro da su. Waɗannan kamar dabbobi suke; a'a, sun ma fi (dabbobi) ɓacewa. Waɗannan su ne gafalallu
(180) Allah kuma Yana da sunaye mafiya kyau, don haka ku roƙe Shi da su; kuma ku rabu da waɗanda suke fanɗarewa game da sunayensa; da sannu za a yi musu sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa
(181) Kuma akwai wata al'umma daga cikin waɗanda Muka halitta suna shiryarwa da gaskiya, kuma da ita suke adalci
(182) Kuma waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu, za Mu yi musu talala ta inda ba su sani ba
(183) Kuma Ina yi musu jinkiri ne; lalle kaidina mai ƙarfi ne
(184) Shin ba za su yi tunani ba. Lalle abokin nasu fa babu hauka a tattare da shi. Ba kowa ne shi ba, face mai gargaɗi, mai bayyanarwa?
(185) Shin ba za su yi duba cikin mulkin sammai da ƙasa da kuma abin da Allah Ya halitta ba, kuma lalle ya kusata a ce ajalinsu yana gab da zuwa, to da wane zance ne za su yi imani bayansa (wato Alƙur'ani)?
(186) Wanda duk Allah Ya ɓatar, to ba shi da mai shiryar da shi. Kuma zai ƙyale su a cikin ƙetare iyakar da suke yi suna ɗimuwa
(187) Suna tambayar ka game da tashin alƙiyama yaushe ne matabbatarta take? Ka ce: "Sanin lokacinta yana wajen Ubangijina; ba mai bayyanar da lokacinta sai Shi. Ta yi nauyi a cikin sammai da ƙasa. Ba za ta zo muku ba sai katsahan." Suna tambayar ka kamar ka nace a kanta, ka ce: "Iliminta yana wajen Allah kaɗai", sai dai da yawa daga cikin mutane ba su sani ba

قُل لَّآ أَمۡلِكُ لِنَفۡسِي نَفۡعٗا وَلَا ضَرًّا إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُۚ وَلَوۡ كُنتُ
أَعۡلَمُ ٱلۡغَيۡبَ لَٱسۡتَكۡثَرۡتُ مِنَ ٱلۡخَيۡرِ وَمَا مَسَّنِيَ ٱلسُّوٓءُۚ
إِنۡ أَنَا۠ إِلَّا نَذِيرٞ وَبَشِيرٞ لِّقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ١٨٨ هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَكُم
مِّن نَّفۡسٖ وَٰحِدَةٖ وَجَعَلَ مِنۡهَا زَوۡجَهَا لِيَسۡكُنَ إِلَيۡهَاۖ فَلَمَّا
تَغَشَّىٰهَا حَمَلَتۡ حَمۡلًا خَفِيفٗا فَمَرَّتۡ بِهِۦۖ فَلَمَّآ أَثۡقَلَت دَّعَوَا
ٱللَّهَ رَبَّهُمَا لَئِنۡ ءَاتَيۡتَنَا صَٰلِحٗا لَّنَكُونَنَّ مِنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ١٨٩
فَلَمَّآ ءَاتَىٰهُمَا صَٰلِحٗا جَعَلَا لَهُۥ شُرَكَآءَ فِيمَآ ءَاتَىٰهُمَاۚ فَتَعَٰلَى
ٱللَّهُ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ١٩٠ أَيُشۡرِكُونَ مَا لَا يَخۡلُقُ شَيۡـٔٗا وَهُمۡ يُخۡلَقُونَ
١٩١ وَلَا يَسۡتَطِيعُونَ لَهُمۡ نَصۡرٗا وَلَآ أَنفُسَهُمۡ يَنصُرُونَ ١٩٢
وَإِن تَدۡعُوهُمۡ إِلَى ٱلۡهُدَىٰ لَا يَتَّبِعُوكُمۡۚ سَوَآءٌ عَلَيۡكُمۡ أَدَعَوۡتُمُوهُمۡ
أَمۡ أَنتُمۡ صَٰمِتُونَ ١٩٣ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ عِبَادٌ
أَمۡثَالُكُمۡۖ فَٱدۡعُوهُمۡ فَلۡيَسۡتَجِيبُواْ لَكُمۡ إِن كُنتُمۡ
صَٰدِقِينَ ١٩٤ أَلَهُمۡ أَرۡجُلٞ يَمۡشُونَ بِهَآ أَمۡ لَهُمۡ أَيۡدٖ يَبۡطِشُونَ
بِهَآ أَمۡ لَهُمۡ أَعۡيُنٞ يُبۡصِرُونَ بِهَآ أَمۡ لَهُمۡ ءَاذَانٞ يَسۡمَعُونَ
بِهَاۗ قُلِ ٱدۡعُواْ شُرَكَآءَكُمۡ ثُمَّ كِيدُونِ فَلَا تُنظِرُونِ ١٩٥

(188) Ka ce, "Ba na iya mallakar wa kaina wani amfani, ko wata cuta sai abin da Allah Ya ga dama. Kuma in da na kasance na san gaibu, lalle da na yawaita alheri, da kuma wani mummunan abu bai shafe ni ba. Ni ba wani ne ba face mai gargaɗi mai bushara ga mutanen da suke yin imani."
(189) Shi ne Wanda Ya halicce ku daga rai guda ɗaya, kuma Ya halicci matarsa daga gare shi, don ya sami nutsuwa tare da ita; to yayin da ya kusance ta, sai ta ɗauki yaron ciki, sai ta ci gaba (da harkokinta) da shi, to yayin da (cikin) ya yi nauyi, sai suka roƙi Allah Ubangijinsu cewa: "Lalle idan Ka ba mu ɗa lafiyayye[1], lalle za mu kasance masu godiya."
(190) To yayin da Ya ba su[2] ɗa lafiyayye, sai suka sanya masa abubuwan tarayya cikin abin da ya ba su. Allah kuwa ya ɗaukaka ga barin abin da suke shirka da Shi
(191) Shin sa riƙa haɗa (Allah) da abin da ba ya halittar komai, hasali ma su ne ake halitta?
(192) Kuma ba za su iya taimaka musu ba, ba kuma za su iya taimaka wa kawunansu ba?
(193) Kuma in da za ku kirawo su zuwa shiriya, to lalle ba za su bi ku ba. Duk ɗaya ne a gare ku kun kirawo su, ko kuma kun yi shiru?
(194) Lalle waɗanda kuke kira ba Allah ba bayi ne kamarku, to ku kirawo su mana, sai su kuma su amsa muku idan kun kasance masu gaskiya ne
(195) Shin wai suna da ƙafafun da suke tafiya da su ne; ko suna da hannayen da suke damƙa da su, ko kuma suna da wasu idanuwa da suke gani da su; ko suna da wasu kunnuwa da suke saurare da su? Ka ce: "Ku kirawo abokan tarayyarku, sannan ku shirya mini makirci kuma kada ku saurara mini."

(1) Watau lafiyayye kuma nagari.

(2) Watau ana nufin cikin zuriyyar Adamu da Hauwa'u waɗanda suka riƙa yi wa Allah kishiyoyi bayan ni'imar da ya yi musu.

إِنَّ وَلِيِّيَ ٱللَّهُ ٱلَّذِي نَزَّلَ ٱلْكِتَٰبَ ۖ وَهُوَ يَتَوَلَّى ٱلصَّٰلِحِينَ
﴿١٩٦﴾ وَٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَسْتَطِيعُونَ نَصْرَكُمْ
وَلَآ أَنفُسَهُمْ يَنصُرُونَ ﴿١٩٧﴾ وَإِن تَدْعُوهُمْ إِلَى ٱلْهُدَىٰ لَا يَسْمَعُوا ۖ
وَتَرَىٰهُمْ يَنظُرُونَ إِلَيْكَ وَهُمْ لَا يُبْصِرُونَ ﴿١٩٨﴾ خُذِ ٱلْعَفْوَ
وَأْمُرْ بِٱلْعُرْفِ وَأَعْرِضْ عَنِ ٱلْجَٰهِلِينَ ﴿١٩٩﴾ وَإِمَّا يَنزَغَنَّكَ
مِنَ ٱلشَّيْطَٰنِ نَزْغٌ فَٱسْتَعِذْ بِٱللَّهِ ۚ إِنَّهُۥ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٢٠٠﴾ إِنَّ
ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوْا۟ إِذَا مَسَّهُمْ طَٰٓئِفٌ مِّنَ ٱلشَّيْطَٰنِ تَذَكَّرُوا۟
فَإِذَا هُم مُّبْصِرُونَ ﴿٢٠١﴾ وَإِخْوَٰنُهُمْ يَمُدُّونَهُمْ فِى ٱلْغَىِّ ثُمَّ
لَا يُقْصِرُونَ ﴿٢٠٢﴾ وَإِذَا لَمْ تَأْتِهِم بِـَٔايَةٍ قَالُوا۟ لَوْلَا ٱجْتَبَيْتَهَا ۚ
قُلْ إِنَّمَآ أَتَّبِعُ مَا يُوحَىٰٓ إِلَىَّ مِن رَّبِّى ۚ هَٰذَا بَصَآئِرُ مِن رَّبِّكُمْ
وَهُدًى وَرَحْمَةٌ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٢٠٣﴾ وَإِذَا قُرِئَ ٱلْقُرْءَانُ
فَٱسْتَمِعُوا۟ لَهُۥ وَأَنصِتُوا۟ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿٢٠٤﴾ وَٱذْكُر رَّبَّكَ
فِى نَفْسِكَ تَضَرُّعًا وَخِيفَةً وَدُونَ ٱلْجَهْرِ مِنَ ٱلْقَوْلِ بِٱلْغُدُوِّ
وَٱلْـَٔاصَالِ وَلَا تَكُن مِّنَ ٱلْغَٰفِلِينَ ﴿٢٠٥﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ عِندَ رَبِّكَ
لَا يَسْتَكْبِرُونَ عَنْ عِبَادَتِهِۦ وَيُسَبِّحُونَهُۥ وَلَهُۥ يَسْجُدُونَ ﴿٢٠٦﴾

(196) "Lalle Majiɓincin lamarina Shi ne Allah Wanda Ya saukar da Littafi; kuma Shi Yake jiɓintar lamarin salihan bayi."
(197) Waɗanda kuke kira ba Shi ba kuwa, ba za su iya taimakon ku ba, kuma ba za su iya taimaka wa kawunansu ba
(198) Kuma idan da za ku yi kiran su zuwa ga shiriya, to fa ba za su ji ba; kuma za ka gan su suna kallon ka, alhali kuwa ba sa gani
(199) Ka yi riƙo da afuwa, kuma ka yi umarni da kyakkyawan abu, ka kuma kawar da kai daga wawaye
(200) Idan wani tunzuri daga Shaiɗan ya tunzura ka, to ka nemi tsarin Allah. Lalle Shi Mai ji ne, Masani
(201) Lalle waɗanda suka kiyaye dokokin Allah, idan wani Shaiɗan mai sa waswasi ya shafe su, sai su tuna (da Allah), sai ga su suna gani tar
(202) 'Yan'uwansu kuwa[1] suna ƙara kawo musu ɗauki na ɓata, sannan su ba sa taƙaitawa
(203) Kuma idan ba ka kawo musu wata aya ba, sai su ce: "Don me ba ka ƙirƙiro ta ba?" Ka ce: "Ba abin da nake bi sai kawai abin da aka yi min wahayinsa daga Ubangijina. Waɗannan hujjoji ne daga Ubangijinku da kuma shiriya da kuma rahama ga mutanen da suke yin imani."
(204) Kuma idan an karanta Alƙur'ani, to ku saurare shi, ku kuma yi tsit, don a ji ƙan ku
(205) Kuma ka ambaci (sunan) Ubangijinka a ranka, kana mai ƙasƙantar da kai, kuma kana mai jin tsoro, ba kuma tare da ɗaga murya ba, safe da yamma, kada kuma ka zamo cikin gafalallu
(206) Lalle waɗanda suke wajen Ubangijinka, ba sa girman kai wajen bautar Sa, kuma suna tsarkake Shi, kuma gare Shi kawai suke yin sujjada

(1) Su ne shaiɗanu na mutane da aljanu, suna ƙara ingiza kafirai cikin ɓata ba tare da suna gajiya ko ƙosawa a kan haka ba.

Sura Anfal

سُورَةُ الأَنفَالِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْأَنفَالِ ۖ قُلِ ٱلْأَنفَالُ لِلَّهِ وَٱلرَّسُولِ ۖ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ
وَأَصْلِحُوا۟ ذَاتَ بَيْنِكُمْ ۖ وَأَطِيعُوا۟ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ إِن كُنتُم
مُّؤْمِنِينَ ﴿١﴾ إِنَّمَا ٱلْمُؤْمِنُونَ ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَجِلَتْ
قُلُوبُهُمْ وَإِذَا تُلِيَتْ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُهُۥ زَادَتْهُمْ إِيمَٰنًا وَعَلَىٰ رَبِّهِمْ
يَتَوَكَّلُونَ ﴿٢﴾ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ
يُنفِقُونَ ﴿٣﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُؤْمِنُونَ حَقًّا ۚ لَّهُمْ دَرَجَٰتٌ عِندَ
رَبِّهِمْ وَمَغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ كَرِيمٌ ﴿٤﴾ كَمَآ أَخْرَجَكَ رَبُّكَ
مِنۢ بَيْتِكَ بِٱلْحَقِّ وَإِنَّ فَرِيقًا مِّنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ لَكَٰرِهُونَ ﴿٥﴾
يُجَٰدِلُونَكَ فِى ٱلْحَقِّ بَعْدَمَا تَبَيَّنَ كَأَنَّمَا يُسَاقُونَ إِلَى ٱلْمَوْتِ
وَهُمْ يَنظُرُونَ ﴿٦﴾ وَإِذْ يَعِدُكُمُ ٱللَّهُ إِحْدَى ٱلطَّآئِفَتَيْنِ أَنَّهَا
لَكُمْ وَتَوَدُّونَ أَنَّ غَيْرَ ذَاتِ ٱلشَّوْكَةِ تَكُونُ لَكُمْ وَيُرِيدُ
ٱللَّهُ أَن يُحِقَّ ٱلْحَقَّ بِكَلِمَٰتِهِۦ وَيَقْطَعَ دَابِرَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٧﴾
لِيُحِقَّ ٱلْحَقَّ وَيُبْطِلَ ٱلْبَٰطِلَ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿٨﴾

(1) Suna tambayar ka game da ganimomi[1]; ka ce (da su): “Ganimomi na Allah ne da kuma Manzo; saboda haka ku kiyaye dokokin Allah, ku kuma gyara tsakaninku, kuma ku bi Allah da Manzonsa, idan kun kasance muminai.”

(2) Muminai na haƙiƙa (su ne) kaɗai waɗanda idan aka ambaci Allah, sai zukatansu su raurawa, idan kuma aka karanta musu ayoyinsa, sai su ƙara musu imani, kuma ga Ubangijinsu ne kawai suke dogara

(3) Waɗanda suke tsayar da salla kuma suke ciyarwa daga abin da muka arzurta su

(4) Waɗannan su ne muminai na haƙiƙa. Suna da muƙamai a wurin Ubangijinsu da kuma gafara da arziki na karamci

(5) Kamar yadda Ubangijinka Ya fitar da kai daga gidanka (na Madina) da gaskiya, alhali lalle wata jama’a daga muminai tabbas suna ƙin (haka)

(6) Suna jayayya da kai game da abin da yake tabbas, kai ka ce ana kora su ne wajen mutuwa, alhali kuwa suna kallo

(7) (Ka tuna) kuma lokacin da Allah Ya yi muku alƙawarin ɗayar jama’an nan guda biyu (na abokan gaba)[2] cewa, lalle taku ce, sai kuka riƙa fatan marar wahalar ce za ta zama taku, alhali kuwa Allah Yana nufin Ya tabbatar da gaskiya da kalmominsa, Ya kuma tumɓuke tushen kafirai

(8) Don (kuma) Ya tabbatar da gaskiya, Ya kuma lalata ɓarna ko da kuwa kafirai sun ƙi (hakan)

(1) Watau tambayar da sahabbai suka yi wa Annabi ( ) game da hukuncin ganimar yaƙin Badar.

(2) Watau ko dai su yi nasarar rutsawa da kayan ayarin fataken Kuraishawa, ko kuma su haɗu da rundunar mayaƙan Makka.

إِذْ تَسْتَغِيثُونَ رَبَّكُمْ فَاسْتَجَابَ لَكُمْ أَنِّي مُمِدُّكُم بِأَلْفٍ
مِّنَ الْمَلَائِكَةِ مُرْدِفِينَ ﴿٩﴾ وَمَا جَعَلَهُ اللَّهُ إِلَّا بُشْرَىٰ
وَلِتَطْمَئِنَّ بِهِ قُلُوبُكُمْ ۚ وَمَا النَّصْرُ إِلَّا مِنْ عِندِ اللَّهِ ۚ إِنَّ اللَّهَ
عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿١٠﴾ إِذْ يُغَشِّيكُمُ النُّعَاسَ أَمَنَةً مِّنْهُ وَيُنَزِّلُ
عَلَيْكُم مِّنَ السَّمَاءِ مَاءً لِّيُطَهِّرَكُم بِهِ وَيُذْهِبَ عَنكُمْ
رِجْزَ الشَّيْطَانِ وَلِيَرْبِطَ عَلَىٰ قُلُوبِكُمْ وَيُثَبِّتَ بِهِ الْأَقْدَامَ
﴿١١﴾ إِذْ يُوحِي رَبُّكَ إِلَى الْمَلَائِكَةِ أَنِّي مَعَكُمْ فَثَبِّتُوا الَّذِينَ
آمَنُوا ۚ سَأُلْقِي فِي قُلُوبِ الَّذِينَ كَفَرُوا الرُّعْبَ فَاضْرِبُوا
فَوْقَ الْأَعْنَاقِ وَاضْرِبُوا مِنْهُمْ كُلَّ بَنَانٍ ﴿١٢﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ
شَاقُّوا اللَّهَ وَرَسُولَهُ ۚ وَمَن يُشَاقِقِ اللَّهَ وَرَسُولَهُ فَإِنَّ اللَّهَ
شَدِيدُ الْعِقَابِ ﴿١٣﴾ ذَٰلِكُمْ فَذُوقُوهُ وَأَنَّ لِلْكَافِرِينَ
عَذَابَ النَّارِ ﴿١٤﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا إِذَا لَقِيتُمُ الَّذِينَ
كَفَرُوا زَحْفًا فَلَا تُوَلُّوهُمُ الْأَدْبَارَ ﴿١٥﴾ وَمَن يُوَلِّهِمْ يَوْمَئِذٍ
دُبُرَهُ إِلَّا مُتَحَرِّفًا لِّقِتَالٍ أَوْ مُتَحَيِّزًا إِلَىٰ فِئَةٍ فَقَدْ بَاءَ
بِغَضَبٍ مِّنَ اللَّهِ وَمَأْوَاهُ جَهَنَّمُ ۖ وَبِئْسَ الْمَصِيرُ ﴿١٦﴾

(9) Ku tuna lokacin da kuke neman taimakon Ubangijinku, sai Ya amsa muku cewa: “Ni zan kawo muku ɗauki na mala’iku dubu masu bibiyar juna.”
(10) Kuma (wannan taimakon) Allah bai sanya shi ba, sai don albishir a gare ku, don kuma zukatanku su nutsu da shi. Babu kuma wata nasara sai daga wurin Allah. Lalle Allah Mabuwayi ne Mai hikima
(11) (Ku kuma tuna) lokacin da gyangyaɗi yake kwashe ku (Allah) Yana Mai amintar da ku (daga tunanin abokan gaba), Ya kuma riƙa saukar da ruwa daga sama don Ya tsarkake ku da shi, Ya kuma tafiyar muku da waswasin shaiɗan, don kuma Ya ƙarfafa zukatanku Ya kuma tabbatar da dugaduganku da shi
(12) (Ka kuma tuna) lokacin da Ubangijinka Yake wahayi zuwa ga mala’iku cewa: “Lalle Ni ina tare da ku, saboda haka ku ƙarfafa wa waɗanda suka yi imani gwiwa. Da sannu zan jefa tsoro cikin zukatan waɗanda suka kafirce, saboda haka ku doki wuyansu, kuma ku doki dukkanin gaɓoɓin hannaye da ƙafafu.”
(13) Wannan kuwa saboda sun saɓa wa Allah da Manzonsa. Duk wanda kuwa ya saɓa wa Allah da Manzonsa to lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne
(14) Wannan (uƙubar) sai ku ɗanɗane ta (a duniya), kuma ba shakka kafirai suna da azabar wuta
(15) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka haɗu da cincirindon waɗanda suka kafirta, to kada ku ba su baya
(16) Duk kuwa wanda ya ba su baya a wannan ranar idan dai ba wanda ya gudu da niyyar juyowa ya kai ɗauki ko kuma mai niyyar haɗuwa da wata jama’a (ta mayaƙa) ba, to haƙiƙa ya komo da fushin Allah, kuma makomarsa Jahannama ce; wannan makoma kuwa ta munana

فَلَمْ تَقْتُلُوهُمْ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ قَتَلَهُمْ ۚ وَمَا رَمَيْتَ إِذْ رَمَيْتَ
وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ رَمَىٰ وَلِيُبْلِيَ ٱلْمُؤْمِنِينَ مِنْهُ بَلَآءً حَسَنًا ۚ
إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿١٧﴾ ذَٰلِكُمْ وَأَنَّ ٱللَّهَ مُوهِنُ كَيْدِ
ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿١٨﴾ إِن تَسْتَفْتِحُوا۟ فَقَدْ جَآءَكُمُ ٱلْفَتْحُ ۖ وَإِن
تَنتَهُوا۟ فَهُوَ خَيْرٌ لَّكُمْ ۖ وَإِن تَعُودُوا۟ نَعُدْ وَلَن تُغْنِىَ عَنكُمْ
فِئَتُكُمْ شَيْـًٔا وَلَوْ كَثُرَتْ وَأَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١٩﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَطِيعُوا۟ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَوَلَّوْا۟ عَنْهُ
وَأَنتُمْ تَسْمَعُونَ ﴿٢٠﴾ وَلَا تَكُونُوا۟ كَٱلَّذِينَ قَالُوا۟ سَمِعْنَا وَهُمْ
لَا يَسْمَعُونَ ﴿٢١﴾ ۞ إِنَّ شَرَّ ٱلدَّوَآبِّ عِندَ ٱللَّهِ ٱلصُّمُّ ٱلْبُكْمُ
ٱلَّذِينَ لَا يَعْقِلُونَ ﴿٢٢﴾ وَلَوْ عَلِمَ ٱللَّهُ فِيهِمْ خَيْرًا لَّأَسْمَعَهُمْ ۖ
وَلَوْ أَسْمَعَهُمْ لَتَوَلَّوا۟ وَّهُم مُّعْرِضُونَ ﴿٢٣﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ ٱسْتَجِيبُوا۟ لِلَّهِ وَلِلرَّسُولِ إِذَا دَعَاكُمْ لِمَا يُحْيِيكُمْ ۖ
وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ يَحُولُ بَيْنَ ٱلْمَرْءِ وَقَلْبِهِۦ وَأَنَّهُۥٓ إِلَيْهِ
تُحْشَرُونَ ﴿٢٤﴾ وَٱتَّقُوا۟ فِتْنَةً لَّا تُصِيبَنَّ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟
مِنكُمْ خَآصَّةً ۖ وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿٢٥﴾

(17) Saboda haka ba ku kuka kashe su ba, Allah ne Ya kashe su[1]. Kuma ba ka jefa ba lokacin da ka jefa, sai dai Allah ne Ya jefa[2]. Don kuma Ya jarrabi muminai da kyakkyawar jarrabawa[3]. Lalle Allah Mai ji ne Masani

(18) Waccan (jarraba ku da aka yi gaskiya ne), kuma lalle Allah Mai raunana makircin kafirai ne

(19) Idan kuna neman zuwan hukunci ne (watau azaba), to haƙiƙa hukuncin ya zo muku. Idan kuka daina to shi ya fi muku alheri, idan kuma kuka koma, to za Mu koma, jama'arku kuma ba za ta amfana muku komai ba, komai yawanta kuwa, lalle kuma Allah Yana tare da muminai

(20) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku bi Allah da Manzonsa kada kuma ku ba shi baya alhali kuwa kuna ji

(21) Kada kuma ku zama kamar waɗanda suka ce: "Mun ji," alhalin kuwa su ba sa ji

(22) Lalle mafi sharrin masu tafiya a bayan ƙasa a wurin Allah (su ne) kurame (ga jin gaskiya) bebaye (ga faɗar gaskiya) waɗanda ba sa hankalta

(23) Da Allah Ya san da akwai wani alheri a tare da su, to da Ya jiyar da su (gaskiya); da kuma Ya jiyar da su ɗin ma, to da kuwa sun ba da baya suna masu bijirewa

(24) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku amsa kiran Allah da na Manzo idan ya yi kiran ku ga abin da zai raya ku; kuma ku sani cewa, lalle Allah Yana kange tsakanin mutum da zuciyarsa, kuma lalle wurinsa ne za a tattara ku

(25) Ku kiyayi fitinar da ba kawai waɗanda suka yi zalunci za ta shafa ba, kuma ku sani cewa lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne

(1) Domin komai ya faru ne da taimakonsa da agajinsa.

(2) Watau shi ma Annabi ( ) da ya xauki qasa da tafin hannunsa ya watsa ta a fuskokin kafirai ta kuma cika musu ido to a haqiqa ba shi ne ya yi wannan jifan ba, Allah ne ya yi.

(3) Domin su yi masa godiya a kan ni'imominsa.

وَٱذْكُرُوٓاْ إِذْ أَنتُمْ قَلِيلٌ مُّسْتَضْعَفُونَ فِى ٱلْأَرْضِ تَخَافُونَ
أَن يَتَخَطَّفَكُمُ ٱلنَّاسُ فَـَٔاوَىٰكُمْ وَأَيَّدَكُم بِنَصْرِهِۦ وَرَزَقَكُم
مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿٢٦﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
لَا تَخُونُواْ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ وَتَخُونُوٓاْ أَمَٰنَٰتِكُمْ وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ
﴿٢٧﴾ وَٱعْلَمُوٓاْ أَنَّمَآ أَمْوَٰلُكُمْ وَأَوْلَٰدُكُمْ فِتْنَةٌ وَأَنَّ ٱللَّهَ
عِندَهُۥٓ أَجْرٌ عَظِيمٌ ﴿٢٨﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن تَتَّقُواْ
ٱللَّهَ يَجْعَل لَّكُمْ فُرْقَانًا وَيُكَفِّرْ عَنكُمْ سَيِّـَٔاتِكُمْ
وَيَغْفِرْ لَكُمْ ۗ وَٱللَّهُ ذُو ٱلْفَضْلِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٢٩﴾ وَإِذْ يَمْكُرُ بِكَ
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لِيُثْبِتُوكَ أَوْ يَقْتُلُوكَ أَوْ يُخْرِجُوكَ ۚ وَيَمْكُرُونَ
وَيَمْكُرُ ٱللَّهُ ۖ وَٱللَّهُ خَيْرُ ٱلْمَٰكِرِينَ ﴿٣٠﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ
ءَايَٰتُنَا قَالُواْ قَدْ سَمِعْنَا لَوْ نَشَآءُ لَقُلْنَا مِثْلَ هَٰذَآ ۙ إِنْ هَٰذَآ
إِلَّآ أَسَٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٣١﴾ وَإِذْ قَالُواْ ٱللَّهُمَّ إِن كَانَ هَٰذَا
هُوَ ٱلْحَقَّ مِنْ عِندِكَ فَأَمْطِرْ عَلَيْنَا حِجَارَةً مِّنَ ٱلسَّمَآءِ
أَوِ ٱئْتِنَا بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿٣٢﴾ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُعَذِّبَهُمْ وَأَنتَ
فِيهِمْ ۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ مُعَذِّبَهُمْ وَهُمْ يَسْتَغْفِرُونَ ﴿٣٣﴾

(26) Kuma ku tuna lokacin da kuke ‘yan tsirari masu rauni a bayan ƙasa, kuna tsoron kada wasu mutane su fauce ku, sai Ya tattara ku (a Madina) Ya kuma ƙarfafa ku da taimakonsa, Ya kuma arzuta ku da tsarkakan abubuwa don ku godiya

(27) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ha’inci Allah da Manzo, (kada) kuma ku ha’inci amanoninku alhali kuna sane

(28) Kuma ku sani cewa, dukiyoyinku da ‘ya’yanku fitina ne, Allah kuma lalle a wurinsa lada mai girma yake

(29) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka kiyaye dokokin Allah, to zai sanya muku (hanyar) tsira Ya kuma kankare muku munanan ayyukanku kuma Ya gafarta muku. Allah kuwa Ma’abocin babbar falala ne

(30) Kuma ka tuna lokacin da waɗanda suka kafirta suke ƙulla maka makirci don su tsare ka ko kuma su kashe ka ko su kore ka. Suna kuma shirya makirci Allah kuma Yana mayar musu sakamakon makircinsu. Allah kuma (Shi ne) Ya fi masu makirci iya (sakayyar) makirci[1]

(31) Idan kuma ana karanta musu ayoyinmu sai su ce: “Haƙiƙa mun ji, ai da mun ga dama ba shakka da mun faɗi irin wannan, wannan ba komai ba ne sai tatsuniyoyin mutanen da.”

(32) Ka tuna kuma lokacin da suka ce: “Ya Allah, idan wannan (Alƙur’ani) ya zamanto gaskiya ne daga wurinka yake, to sai Ka yi mana ruwan duwatsu daga sama ko kuma Ka kawo mana da wata azaba mai raɗaɗi.”

(33) Allah kuwa bai zamanto Mai yi musu azaba ba alhali kai kana cikinsu, kuma Allah ba zai yi musu azaba ba alhali suna neman gafara

(1) Wannan bayani ne game da makircin da shugabannin Kuraishawa suka shirya wa Annabi ( ) a Makka kafin ya yi hijira zuwa Madina.

وَمَا لَهُمْ أَلَّا يُعَذِّبَهُمُ ٱللَّهُ وَهُمْ يَصُدُّونَ عَنِ ٱلْمَسْجِدِ
ٱلْحَرَامِ وَمَا كَانُوٓا۟ أَوْلِيَآءَهُۥٓ ۚ إِنْ أَوْلِيَآؤُهُۥٓ إِلَّا ٱلْمُتَّقُونَ
وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٣٤﴾ وَمَا كَانَ صَلَاتُهُمْ
عِندَ ٱلْبَيْتِ إِلَّا مُكَآءً وَتَصْدِيَةً ۚ فَذُوقُوا۟ ٱلْعَذَابَ
بِمَا كُنتُمْ تَكْفُرُونَ ﴿٣٥﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ يُنفِقُونَ
أَمْوَٰلَهُمْ لِيَصُدُّوا۟ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ ۚ فَسَيُنفِقُونَهَا ثُمَّ تَكُونُ
عَلَيْهِمْ حَسْرَةً ثُمَّ يُغْلَبُونَ ۗ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ إِلَىٰ جَهَنَّمَ
يُحْشَرُونَ ﴿٣٦﴾ لِيَمِيزَ ٱللَّهُ ٱلْخَبِيثَ مِنَ ٱلطَّيِّبِ وَيَجْعَلَ
ٱلْخَبِيثَ بَعْضَهُۥ عَلَىٰ بَعْضٍ فَيَرْكُمَهُۥ جَمِيعًا فَيَجْعَلَهُۥ
فِى جَهَنَّمَ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْخَٰسِرُونَ ﴿٣٧﴾ قُل لِّلَّذِينَ
كَفَرُوٓا۟ إِن يَنتَهُوا۟ يُغْفَرْ لَهُم مَّا قَدْ سَلَفَ وَإِن يَعُودُوا۟
فَقَدْ مَضَتْ سُنَّتُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٣٨﴾ وَقَٰتِلُوهُمْ حَتَّىٰ
لَا تَكُونَ فِتْنَةٌ وَيَكُونَ ٱلدِّينُ كُلُّهُۥ لِلَّهِ ۚ فَإِنِ
ٱنتَهَوْا۟ فَإِنَّ ٱللَّهَ بِمَا يَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿٣٩﴾ وَإِن تَوَلَّوْا۟
فَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ مَوْلَىٰكُمْ ۚ نِعْمَ ٱلْمَوْلَىٰ وَنِعْمَ ٱلنَّصِيرُ ﴿٤٠﴾

(34) Me zai hana Allah Ya yi musu azaba alhali su suna hana mutane zuwa Masallaci mai alfarma, alhali kuwa ba su zamanto masu ƙaunar Sa na haƙiƙa ba. Masu ƙaunar Sa na haƙiƙa su ne masu taƙawa, sai dai yawancinsu ba sa sanin (haka)

(35) Kuma sallarsu a Ɗakin (Ka'aba) ba ta zamanto ba sai fito da tafi. Sai ku ɗanɗani azaba saboda abin da kuka zamanto kuna yi na kafirci

(36) Lalle waɗanda suka kafirta suna kashe dukiyoyinsu don su toshe hanyar Allah. To da sannu za su kashe ta (dukiyar) sannan ta zama nadama a gare su, sannan kuma a rinjaye su. Waɗanda kuwa suka kafirta a Jahannama za a tattara su

(37) Don Allah Ya ware mummuna daga kyakkyawa, Ya kuma haɗa mummuna wani a kan wani, sannan Ya tattara shi gaba ɗaya cikin Jahannama. Waɗannan su ne asararru


(38) Ka ce da waɗanda suka kafirta idan suka daina, to za a gafarta musu abin da ya riga ya wuce, idan kuma suka koma to fa ba shakka al'adar mutanen farko ta gabata[1]

(39) Kuma ku yaƙe su har sai ya zamanto ba wata fitina[2], addini kuma ya zamanto dukkaninsa na Allah. Sannan idan suka daina, to lalle Allah Mai ganin abin da suke aikatawa ne

(40) Idan kuma suka ba da baya, to ku sani cewa, Allah (Shi ne) Majiɓincin al'amarinku. Madalla da wannan Majiɓinci, kuma madalla da wannan Mai taimako

(1) Watau yadda Allah ( ) ya hallaka al'ummun da suka gabata waɗanda suka ƙaryata annabawansu.

(2) Watau watsuwar shirka a cikin al'umma da yunƙurin hana mutane karɓar gaskiya.



وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّمَا غَنِمْتُم مِّن شَىْءٍ فَأَنَّ لِلَّهِ خُمُسَهُۥ وَلِلرَّسُولِ
وَلِذِى ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينِ وَٱبْنِ ٱلسَّبِيلِ إِن
كُنتُمْ ءَامَنتُم بِٱللَّهِ وَمَآ أَنزَلْنَا عَلَىٰ عَبْدِنَا يَوْمَ ٱلْفُرْقَانِ
يَوْمَ ٱلْتَقَى ٱلْجَمْعَانِ ۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٤١﴾ إِذْ
أَنتُم بِٱلْعُدْوَةِ ٱلدُّنْيَا وَهُم بِٱلْعُدْوَةِ ٱلْقُصْوَىٰ وَٱلرَّكْبُ
أَسْفَلَ مِنكُمْ ۚ وَلَوْ تَوَاعَدتُّمْ لَٱخْتَلَفْتُمْ فِى ٱلْمِيعَٰدِ
وَلَٰكِن لِّيَقْضِىَ ٱللَّهُ أَمْرًا كَانَ مَفْعُولًا لِّيَهْلِكَ مَنْ
هَلَكَ عَنۢ بَيِّنَةٍ وَيَحْيَىٰ مَنْ حَىَّ عَنۢ بَيِّنَةٍ ۗ وَإِنَّ ٱللَّهَ
لَسَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٤٢﴾ إِذْ يُرِيكَهُمُ ٱللَّهُ فِى مَنَامِكَ قَلِيلًا ۖ
وَلَوْ أَرَىٰكَهُمْ كَثِيرًا لَّفَشِلْتُمْ وَلَتَنَٰزَعْتُمْ فِى ٱلْأَمْرِ
وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ سَلَّمَ ۗ إِنَّهُۥ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿٤٣﴾ وَإِذْ
يُرِيكُمُوهُمْ إِذِ ٱلْتَقَيْتُمْ فِىٓ أَعْيُنِكُمْ قَلِيلًا وَيُقَلِّلُكُمْ
فِىٓ أَعْيُنِهِمْ لِيَقْضِىَ ٱللَّهُ أَمْرًا كَانَ مَفْعُولًا ۗ وَإِلَى ٱللَّهِ
تُرْجَعُ ٱلْأُمُورُ ﴿٤٤﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِذَا لَقِيتُمْ فِئَةً
فَٱثْبُتُوا۟ وَٱذْكُرُوا۟ ٱللَّهَ كَثِيرًا لَّعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿٤٥﴾

(41) Kuma ku sani cewa duk abin da kuka samu na ganima to lalle ɗaya bisa biyar na Allah ne da Manzo da kuma makusantan (Annabi)[1], da marayu da kuma miskinai da kuma matafiya[2], idan kun kasance kun yi imani da Allah da kuma abin da Muka saukar wa bawanmu ranar rabewa (ranar yaƙin Badar) ranar da ƙungiyoyin nan biyu suka haɗu. Allah kuwa Mai iko ne a kan komai

(42) Ku tuna lokacin da kuke a gacin da ya fi kusa (da Madina) su kuma suna gacin da ya fi nisa, ayarin (Abu Sufyan) kuwa yana ƙasa da ku. Da kuwa kun yi alƙawarin (haɗuwa a Badar) to babu shakka da kun saɓa wajen cika alƙawarin, sai dai kuma wannan ya faru ne saboda Allah Ya zartar da al'amarin da ya zamanto mai faruwa ne, don wanda ya hallaka ya hallaka da dalili, kuma wanda kuma ya rayu ya rayu da dalili. Lalle Allah Mai ji ne Masani

(43) Ka tuna lokacin da Allah Yake nuna maka su cikin baccinka suna 'yan kaɗan; da kuwa Ya nuna maka su da yawa fal, to ba shakka da kun tsorata kuma lalle da kun yi jayayya a cikin al'amarin, sai dai kuma Allah Ya kiyaye. Lalle Shi Masanin abin da ke zukata ne

(44) Ku kuma tuna lokacin da Yake nuna muku su a yayin da kuka gamu suna 'yan kaɗan a idanuwanku, Yake kuma ƙarantar da ku a idonsu, saboda Allah Ya hukunta al'amarin da yake mai afkuwa ne. Kuma wurin Allah ne ake mayar da duka al'amura

(45) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka haɗu da wata ƙungiya (ta mayaƙa), to sai ku dage, ku kuma ambaci Allah da yawa, don ku rabauta

(1) Su ne Banu Hashim da Banu Muɗɗalib waɗanda aka haramta musu cin zakka.

(2) Suran kashi huɗun kuwa na mayaƙa ne.

وَأَطِيعُوا۟ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَنَٰزَعُوا۟ فَتَفْشَلُوا۟ وَتَذْهَبَ
رِيحُكُمْ ۖ وَٱصْبِرُوٓا۟ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ﴿٤٦﴾ وَلَا تَكُونُوا۟
كَٱلَّذِينَ خَرَجُوا۟ مِن دِيَٰرِهِم بَطَرًا وَرِئَآءَ ٱلنَّاسِ وَيَصُدُّونَ
عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا يَعْمَلُونَ مُحِيطٌ ﴿٤٧﴾ وَإِذْ زَيَّنَ
لَهُمُ ٱلشَّيْطَٰنُ أَعْمَٰلَهُمْ وَقَالَ لَا غَالِبَ لَكُمُ ٱلْيَوْمَ مِنَ
ٱلنَّاسِ وَإِنِّى جَارٌ لَّكُمْ ۖ فَلَمَّا تَرَٰٓءَتِ ٱلْفِئَتَانِ نَكَصَ
عَلَىٰ عَقِبَيْهِ وَقَالَ إِنِّى بَرِىٓءٌ مِّنكُمْ إِنِّىٓ أَرَىٰ مَا لَا
تَرَوْنَ إِنِّىٓ أَخَافُ ٱللَّهَ ۚ وَٱللَّهُ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿٤٨﴾ إِذْ يَقُولُ
ٱلْمُنَٰفِقُونَ وَٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ غَرَّ هَٰٓؤُلَآءِ دِينُهُمْ ۗ
وَمَن يَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٤٩﴾ وَلَوْ
تَرَىٰٓ إِذْ يَتَوَفَّى ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَضْرِبُونَ
وُجُوهَهُمْ وَأَدْبَٰرَهُمْ وَذُوقُوا۟ عَذَابَ ٱلْحَرِيقِ ﴿٥٠﴾ ذَٰلِكَ
بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيكُمْ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَيْسَ بِظَلَّٰمٍ لِّلْعَبِيدِ ﴿٥١﴾
كَدَأْبِ ءَالِ فِرْعَوْنَ وَٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ ۚ كَفَرُوا۟ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ
فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ بِذُنُوبِهِمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ قَوِىٌّ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿٥٢﴾

(46) Kuma ku bi Allah da Manzonsa, kada ku rarrabu sai ku zama matsorata kuma ƙarfinku ya tafi; ku kuma yi haƙuri. Lalle Allah Yana tare da masu haƙuri
(47) Kada kuma ku zama kamar waɗanda suka fito daga gidajensu don fariya da kuma nuna wa mutane (watau riya), suna kuma hana (mutane) bin hanyar Allah. Allah kuwa Mai kewaye abin da suke aikatawa ne
(48) Kuma ku tuna lokacin da Shaiɗan ya ƙawata musu ayyukansu, ya kuma ce: "Babu wasu mutane a yau da za su yi galaba a kanku, lalle kuma ni maƙocinku ne." Saboda haka lokacin da ƙungiyoyin biyu suka haɗu sai ya tsere a guje, ya kuma ce: "Lalle ni ba ruwana da ku, lalle ni ina ganin abin da ku ba kwa gani, lalle ni ina tsoron Allah. Allah kuwa Mai tsananin azaba ne."
(49) Ka tuna lokacin da munafuƙai da kuma waɗanda suke da rauni a zukatansu suke cewa: "Waɗannan addininsu ne ya ruɗe su." Duk wanda ya dogara ga Allah kuwa to lalle Allah Mabuwayi ne Mai hikima
(50) Kuma da za ka ga lokacin da mala'iku suke ɗaukan ran waɗanda suka kafirta, suna dukan fuskokinsu da kuma bayansu, suna kuma (cewa da su): "Ku ɗanɗani azabar ƙuna."
(51) "Wannan (ya faru gare ku ne) saboda abin da hannayenku suka aikata, kuma lalle Allah ba Mai zaluntar bayi ne ba."
(52) (Al'adar kafiran Makka) kamar al'adar mutanen Fir'auna ce da kuma waɗanda suke gabaninsu. Sun kafirce wa ayoyin Allah, saboda haka Allah Ya kama su da zunubansu. Lalle Allah Mai ƙarfi ne, Mai tsananin uƙuba

ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ لَمۡ يَكُ مُغَيِّرٗا نِّعۡمَةً أَنۡعَمَهَا عَلَىٰ قَوۡمٍ حَتَّىٰ
يُغَيِّرُواْ مَا بِأَنفُسِهِمۡ وَأَنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ٥٣ كَدَأۡبِ ءَالِ
فِرۡعَوۡنَ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمۡ فَأَهۡلَكۡنَٰهُم
بِذُنُوبِهِمۡ وَأَغۡرَقۡنَآ ءَالَ فِرۡعَوۡنَۚ وَكُلّٞ كَانُواْ ظَٰلِمِينَ ٥٤
إِنَّ شَرَّ ٱلدَّوَآبِّ عِندَ ٱللَّهِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ
٥٥ ٱلَّذِينَ عَٰهَدتَّ مِنۡهُمۡ ثُمَّ يَنقُضُونَ عَهۡدَهُمۡ فِي كُلِّ
مَرَّةٖ وَهُمۡ لَا يَتَّقُونَ ٥٦ فَإِمَّا تَثۡقَفَنَّهُمۡ فِي ٱلۡحَرۡبِ فَشَرِّدۡ بِهِم
مَّنۡ خَلۡفَهُمۡ لَعَلَّهُمۡ يَذَّكَّرُونَ ٥٧ وَإِمَّا تَخَافَنَّ مِن قَوۡمٍ
خِيَانَةٗ فَٱنۢبِذۡ إِلَيۡهِمۡ عَلَىٰ سَوَآءٍۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلۡخَآئِنِينَ
٥٨ وَلَا يَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ سَبَقُوٓاْۚ إِنَّهُمۡ لَا يُعۡجِزُونَ
٥٩ وَأَعِدُّواْ لَهُم مَّا ٱسۡتَطَعۡتُم مِّن قُوَّةٖ وَمِن رِّبَاطِ ٱلۡخَيۡلِ
تُرۡهِبُونَ بِهِۦ عَدُوَّ ٱللَّهِ وَعَدُوَّكُمۡ وَءَاخَرِينَ مِن دُونِهِمۡ
لَا تَعۡلَمُونَهُمۡ ٱللَّهُ يَعۡلَمُهُمۡۚ وَمَا تُنفِقُواْ مِن شَيۡءٖ فِي سَبِيلِ
ٱللَّهِ يُوَفَّ إِلَيۡكُمۡ وَأَنتُمۡ لَا تُظۡلَمُونَ ٦٠ ۞ وَإِن جَنَحُواْ لِلسَّلۡمِ
فَٱجۡنَحۡ لَهَا وَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٦١

(53) Wannan (kuwa) saboda Allah bai kasance Mai canza wata ni'ima da Ya yi wa wasu mutane ba har sai sun canja halayensu, lalle Allah kuma Mai ji ne Masani
(54) Kamar al'adar mutanen Fir'auna ce da kuma waɗanda suke gabaninsu. Sun ƙaryata ayoyin Ubangijinsu, sai Muka hallaka su saboda zunubansu, Muka kuma nutsar da mutanen Fir'auna (a cikin kogi). Dukkaninsu kuwa sun kasance azzalumai
(55) Lalle mafi sharrin masu tafiya a bayan ƙasa a wurin Allah (su ne) waɗanda suka kafirta, don haka kuma su ba sa yin imani
(56) Waɗanda idan ka yi alƙawari da su sai su warware alƙawarinsu ko da yaushe, ba sa kuma kiyaye dokokin Allah (dangane da alƙawari)
(57) Sannan idan ka haɗu da su a wurin yaƙi, to sai ka fatattaki na bayansu da su, don su (na bayan) sa wa'azantu
(58) Kuma idan kana jin tsoron wani ha'inci daga wasu mutane (da ka yi sulhu da su), to sai ka jefar musu shi (sulhun) a bayyane (ba da ha'inci ba). Lalle Allah ba Ya son masu ha'inci
(59) Kuma kada waɗanda suka kafirta su yi tsammanin sun tsere, lalle su ba za su gagari (Allah) ba
(60) Ku yi musu tanadin abin da kuke iyawa na ƙarfi da kuma tanadin ɗaurarrun dawakai, kuna tsorata maƙiya Allah kuma maƙiyanku da shi (tanadin), har kuma da wasu ban da su da ba ku san su ba, Allah ne kawai Ya san su. Kuma duk irin abin da kuka ciyar cikin hanyar Allah za a cika muku (ladanku) ba kuwa za a zalunce ku ba
(61) Idan kuma suka karkato ga sulhu, to sai kai ma ka karkato gare shi, ka kuma dogara ga Allah. Lalle Shi Mai ji ne Masani

وَإِن يُرِيدُوٓاْ أَن يَخۡدَعُوكَ فَإِنَّ حَسۡبَكَ ٱللَّهُۚ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَيَّدَكَ
بِنَصۡرِهِۦ وَبِٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٦٢ وَأَلَّفَ بَيۡنَ قُلُوبِهِمۡۚ لَوۡ أَنفَقۡتَ
مَا فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا مَّآ أَلَّفۡتَ بَيۡنَ قُلُوبِهِمۡ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ
أَلَّفَ بَيۡنَهُمۡۚ إِنَّهُۥ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ٦٣ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ حَسۡبُكَ
ٱللَّهُ وَمَنِ ٱتَّبَعَكَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٦٤ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ حَرِّضِ
ٱلۡمُؤۡمِنِينَ عَلَى ٱلۡقِتَالِۚ إِن يَكُن مِّنكُمۡ عِشۡرُونَ صَٰبِرُونَ
يَغۡلِبُواْ مِاْئَتَيۡنِۚ وَإِن يَكُن مِّنكُم مِّاْئَةٞ يَغۡلِبُوٓاْ أَلۡفٗا مِّنَ
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ لَّا يَفۡقَهُونَ ٦٥ ٱلۡـَٰٔنَ خَفَّفَ
ٱللَّهُ عَنكُمۡ وَعَلِمَ أَنَّ فِيكُمۡ ضَعۡفٗاۚ فَإِن يَكُن مِّنكُم مِّاْئَةٞ
صَابِرَةٞ يَغۡلِبُواْ مِاْئَتَيۡنِۚ وَإِن يَكُن مِّنكُمۡ أَلۡفٞ يَغۡلِبُوٓاْ
أَلۡفَيۡنِ بِإِذۡنِ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ٦٦ مَا كَانَ لِنَبِيٍّ
أَن يَكُونَ لَهُۥٓ أَسۡرَىٰ حَتَّىٰ يُثۡخِنَ فِي ٱلۡأَرۡضِۚ تُرِيدُونَ عَرَضَ
ٱلدُّنۡيَا وَٱللَّهُ يُرِيدُ ٱلۡأٓخِرَةَۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ٦٧ لَّوۡلَا كِتَٰبٞ
مِّنَ ٱللَّهِ سَبَقَ لَمَسَّكُمۡ فِيمَآ أَخَذۡتُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ٦٨ فَكُلُواْ
مِمَّا غَنِمۡتُمۡ حَلَٰلٗا طَيِّبٗاۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٦٩

(62) Idan kuma suka yi niyyar yaudarar ka, to lalle Allah Ya ishe ka. Shi ne wanda Ya ƙarfafe ka da taimakonsa da kuma muminai

(63) Ya kuma haɗa tsakanin zukatansu. Idan da za ka kashe duk abin da yake bayan ƙasa gaba ɗaya ba za ka iya haɗa tsakanin zukatansu ba, amma kuma Allah Ya haɗe tsakaninsu. Lalle Shi Mabuwayi ne Mai hikima

(64) Ya kai wannan Annabi, Allah Ya ishe ka, kai da kuma muminai waɗanda suka bi ka

(65) Ya kai wannan Annabi, ka zaburar da muminai a kan yaƙi. Idan daga cikinku akwai (mutum) ashirin masu haƙuri to za su rinjayi (mutum) ɗari biyu (kafirai). Idan kuma daga cikinku akwai (mutum) ɗari to za su rinjayi (mutum) dubu daga waɗanda suka kafirta, saboda su mutane ne da ba sa ganewa

(66) Yanzu Allah Ya sassauta muku, Ya kuma san cewa a cikinku akwai raunana, saboda haka idan ya zamanto a cikinku akwai (mutum) ɗari masu haƙuri to za su rinjayi (mutum) ɗari biyu (kafirai). Idan kuma ya kasance akwai (mutum) dubu daga cikinku to za su rinjayi (kafirai) dubu biyu da izinin Allah. Allah kuma Yana tare da masu haƙuri

(67) Bai kamata ga wani annabi ya kasance yana da wasu fursunonin yaƙi ba har sai ya yi kisan (abokan gaba) sosai a bayan ƙasa. Kuna nufin abin duniya Allah kuma Yana nufin lahira. Allah kuwa Mabuwayi ne Mai hikima

(68) Ba don wani hukunci ya riga ya gabata daga Allah ba[1], tabbas da azaba mai girma ta shafe ku game da abin da kuka karɓa (na fansa)

(69) To sai ku ci daga abin da kuka samu na ganima halal, tsattsarka. Kuma ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(1) Watau da cewa, Allah ba ya kama muminai da kuskuren da suka yi wajen ƙoƙarin gano hukuncin Allah, sannan ya riga ya yafe wa duk muminan da suka je yaƙin Badar.

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ قُل لِّمَن فِيٓ أَيۡدِيكُم مِّنَ ٱلۡأَسۡرَىٰٓ إِن يَعۡلَمِ ٱللَّهُ
فِي قُلُوبِكُمۡ خَيۡرٗا يُؤۡتِكُمۡ خَيۡرٗا مِّمَّآ أُخِذَ مِنكُمۡ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۚ
وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٧٠ وَإِن يُرِيدُواْ خِيَانَتَكَ فَقَدۡ خَانُواْ ٱللَّهَ
مِن قَبۡلُ فَأَمۡكَنَ مِنۡهُمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ٧١ إِنَّ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡ فِي سَبِيلِ
ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٖۚ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَلَمۡ يُهَاجِرُواْ مَا لَكُم مِّن وَلَٰيَتِهِم مِّن شَيۡءٍ حَتَّىٰ يُهَاجِرُواْۚ
وَإِنِ ٱسۡتَنصَرُوكُمۡ فِي ٱلدِّينِ فَعَلَيۡكُمُ ٱلنَّصۡرُ إِلَّا عَلَىٰ قَوۡمِۭ
بَيۡنَكُمۡ وَبَيۡنَهُم مِّيثَٰقٞۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ٧٢ وَٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٍۚ إِلَّا تَفۡعَلُوهُ تَكُن فِتۡنَةٞ فِي
ٱلۡأَرۡضِ وَفَسَادٞ كَبِيرٞ ٧٣ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ
فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ
حَقّٗاۚ لَّهُم مَّغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ٧٤ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنۢ بَعۡدُ
وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ مَعَكُمۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ مِنكُمۡۚ وَأُوْلُواْ ٱلۡأَرۡحَامِ
بَعۡضُهُمۡ أَوۡلَىٰ بِبَعۡضٖ فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمُۢ ٧٥

(70) Ya kai wannan Annabi, ka ce da fursunonin da suke a hannayenku: “Idan dai har Allah Ya san akwai wani alheri a zukatanku, to zai ba ku fiye da abin da aka karba daga wurinku Ya kuma gafarta muku. Allah kuwa Mai gafara ne Mai jin kai.”
(71) Idan kuwa suna nufin ha’intar ka ne, to hakika da can ma sun ha’inci Allah, saboda haka Ya dora (ka) a kansu. Allah kuwa Masani ne Mai hikima
(72) Lalle waɗanda suka yi imani kuma suka yi hijira, suka kuma yi yaƙi da dukiyoyinsu da kuma rayukansu don Allah, da waɗanda kuma suka sauki (muminai masu hijira) suka kuma taimaka (wajen yaƙi), to waɗannan masu ƙaunar juna ne. Waɗanda kuma suka yi imani ba su kuma yi hijira ba, to babu jiɓintar al’amari a tsakaninku har sai sun yi hijira. Idan kuma suka nemi taimakonku cikin (al’amarin) addini to lalle ne ku taimake su, sai dai idan game da wasu mutane ne waɗanda yake da akwai wani alƙawari a tsakaninku da su. Allah kuma Mai ganin abin da kuke aikatawa ne
(73) Waɗanda kuwa suka kafirta, su masu ƙaunar juna ne. Idan ku ma ba ku aikata haka ba, to za a samu wata fitina a bayan ƙasa da kuma wata ɓarna mai girma
(74) Waɗanda kuma suka yi imani kuma suka yi hijira suka kuma yi yaƙi saboda Allah, da waɗanda kuma suka sauki (masu hijira) suka kuma taimaka, waɗannan su ne muminai na gaskiya. Suna da (sakamakon) gafara da kuma arziki na karamci
(75) Waɗanda kuma suka yi imani daga baya, suka kuma yi hijira, suka kuma yi yaƙi tare da ku, to waɗannan suna cikinku. ‘Yan’uwa na jini kuma su ne suka fi cancantar (gadon) junansu a cikin Littafin Allah. Lalle Allah Masani ne ga komai

Sura Tauba

سُورَةُ التَّوۡبَةِ

بَرَآءَةٞ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦٓ إِلَى ٱلَّذِينَ عَٰهَدتُّم مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ١
فَسِيحُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ أَرۡبَعَةَ أَشۡهُرٖ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّكُمۡ غَيۡرُ مُعۡجِزِي
ٱللَّهِ وَأَنَّ ٱللَّهَ مُخۡزِي ٱلۡكَٰفِرِينَ ٢ وَأَذَٰنٞ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦٓ
إِلَى ٱلنَّاسِ يَوۡمَ ٱلۡحَجِّ ٱلۡأَكۡبَرِ أَنَّ ٱللَّهَ بَرِيٓءٞ مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ
وَرَسُولُهُۥۚ فَإِن تُبۡتُمۡ فَهُوَ خَيۡرٞ لَّكُمۡۖ وَإِن تَوَلَّيۡتُمۡ فَٱعۡلَمُوٓاْ
أَنَّكُمۡ غَيۡرُ مُعۡجِزِي ٱللَّهِۗ وَبَشِّرِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِعَذَابٍ أَلِيمٍ
٣ إِلَّا ٱلَّذِينَ عَٰهَدتُّم مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ثُمَّ لَمۡ يَنقُصُوكُمۡ شَيۡـٔٗا
وَلَمۡ يُظَٰهِرُواْ عَلَيۡكُمۡ أَحَدٗا فَأَتِمُّوٓاْ إِلَيۡهِمۡ عَهۡدَهُمۡ إِلَىٰ مُدَّتِهِمۡۚ
إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُتَّقِينَ ٤ فَإِذَا ٱنسَلَخَ ٱلۡأَشۡهُرُ ٱلۡحُرُمُ
فَٱقۡتُلُواْ ٱلۡمُشۡرِكِينَ حَيۡثُ وَجَدتُّمُوهُمۡ وَخُذُوهُمۡ وَٱحۡصُرُوهُمۡ
وَٱقۡعُدُواْ لَهُمۡ كُلَّ مَرۡصَدٖۚ فَإِن تَابُواْ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ
ٱلزَّكَوٰةَ فَخَلُّواْ سَبِيلَهُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٥ وَإِنۡ أَحَدٞ
مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ٱسۡتَجَارَكَ فَأَجِرۡهُ حَتَّىٰ يَسۡمَعَ كَلَٰمَ
ٱللَّهِ ثُمَّ أَبۡلِغۡهُ مَأۡمَنَهُۥۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ لَّا يَعۡلَمُونَ ٦

(1) Allah da Manzonsa ba ruwansu da wadanda kuka yi alkawari da su daga cikin mushirikai[1]
(2) To sai ku tafi ku wala a bayan kasa tsawon wata hudu, kuma ku sani cewa ku ba za ku gagari Allah ba, kuma lalle Allah Mai wulakanta kafirai ne
(3) Kuma sanarwa daga Allah da Manzonsa zuwa ga mutane ranar Babbar Salla cewa, lalle Allah da Manzonsa babu ruwansu da mushrikai[2]. Amma idan kuka tuba, to shi ya fi alheri a gare ku, idan kuma kuka ba da baya, to ku sani lalle ku fa ba za ku gagari Allah ba. Kuma ka yi albishir ga wadanda suka kafirta da azaba mai radadi
(4) Sai fa wadannan mushrikan da kuka yi alkawari da su sannan kuma ba su rage muku wani abu ba (daga alkawarin), ba su kuma taimaka wa wani a kanku ba, to sai ku cika musu alkawarinsu har zuwa lokacinsu (da kuka ayyana). Lalle Allah Yana son masu takawa
(5) To idan watanni masu alfarma suka wuce[3] sai ku yaki mushrikai a duk inda kuka same su, ku kuma kama su ku tsare su ku kuma toshe musu kowace hanya. To amma idan sun tuba sun kuma tsai da salla kuma sun ba da zakka, to sai ku kyale su. Lalle Allah Mai gafara ne Mai jin kai
(6) Kuma idan wani daga mushrikai ya nemi mafaka a wurinka to sai ka ba shi mafaka har ya samu damar jin zancen Allah, sannan ka isar da shi wurin amincewarsa. Wannan kuwa saboda lalle su mutane ne da ba sa sanin (gaskiya)

(1) Watau wadanda suka warware alkawarinsu.

(2) A shekara ta tara bayan hijira, Annabi ( ) ya aika Abubakar da Aliyyu ( ) su yi shela a Makka a ranar sallar layya cewa, kada wani mushiriki ya sake zuwa hajji ko ya yi dawafi tsirara.

(3) Su ne watanni hudu masu alfarma, watau Zulki'ida da Zulhijja da Al-Muharram da Rajab.

كَيْفَ يَكُونُ لِلْمُشْرِكِينَ عَهْدٌ عِندَ ٱللَّهِ وَعِندَ رَسُولِهِۦٓ
إِلَّا ٱلَّذِينَ عَٰهَدتُّمْ عِندَ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ ۖ فَمَا ٱسْتَقَٰمُوا۟
لَكُمْ فَٱسْتَقِيمُوا۟ لَهُمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُتَّقِينَ ﴿٧﴾
كَيْفَ وَإِن يَظْهَرُوا۟ عَلَيْكُمْ لَا يَرْقُبُوا۟ فِيكُمْ إِلًّا وَلَا
ذِمَّةً ۚ يُرْضُونَكُم بِأَفْوَٰهِهِمْ وَتَأْبَىٰ قُلُوبُهُمْ وَأَكْثَرُهُمْ
فَٰسِقُونَ ﴿٨﴾ ٱشْتَرَوْا۟ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ ثَمَنًا قَلِيلًا فَصَدُّوا۟ عَن
سَبِيلِهِۦٓ ۚ إِنَّهُمْ سَآءَ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٩﴾ لَا يَرْقُبُونَ
فِى مُؤْمِنٍ إِلًّا وَلَا ذِمَّةً ۚ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُعْتَدُونَ ﴿١٠﴾ فَإِن
تَابُوا۟ وَأَقَامُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُا۟ ٱلزَّكَوٰةَ فَإِخْوَٰنُكُمْ فِى
ٱلدِّينِ ۗ وَنُفَصِّلُ ٱلْـَٔايَٰتِ لِقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ﴿١١﴾ وَإِن
نَّكَثُوٓا۟ أَيْمَٰنَهُم مِّنۢ بَعْدِ عَهْدِهِمْ وَطَعَنُوا۟ فِى دِينِكُمْ
فَقَٰتِلُوٓا۟ أَئِمَّةَ ٱلْكُفْرِ ۙ إِنَّهُمْ لَآ أَيْمَٰنَ لَهُمْ لَعَلَّهُمْ
يَنتَهُونَ ﴿١٢﴾ أَلَا تُقَٰتِلُونَ قَوْمًا نَّكَثُوٓا۟ أَيْمَٰنَهُمْ
وَهَمُّوا۟ بِإِخْرَاجِ ٱلرَّسُولِ وَهُم بَدَءُوكُمْ أَوَّلَ مَرَّةٍ ۚ
أَتَخْشَوْنَهُمْ ۚ فَٱللَّهُ أَحَقُّ أَن تَخْشَوْهُ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٣﴾

(7) Ta yaya zai yiwu a samu wani alƙawari tsakanin Allah da Manzonsa da kuma mushirikai in ban da waɗanda kuka yi alƙawari da su a Masallaci mai alfarma? To matuƙar sun tsaya muku (bisa gaskiya) sai ku ma ku tsaya musu. Lalle Allah Yana son masu taƙawa

(8) Ta yaya?! (haka zai faru) alhali idan suka yi nasara a kanku ba za su duba wani kusanci ba balle wani alƙawari game da ku? Suna yardar da ku ne da bakunansu, alhali kuwa zukatansu suna ƙi.

Yawancinsu kuma fasiƙai ne

(9) Sun musanya ayoyin Allah da ɗan kuɗi ƙanƙani, sannan suka toshe hanyarsa. Lalle su dai abin da suke aikatawa ya munana

(10) Ba sa duban wani kusanci na zumunci da wani mumini ballantana kuma wani alƙawari. Waɗannan kuma su ne masu ƙetare iyaka

(11) To idan sun tuba, suka kuma tsayar da salla kuma suka ba da zakka, to sun zama 'yan'uwanku a cikin addini. Muna kuwa bayanin ayoyi ne filla-filla ga mutane da suke da sani

(12) Idan kuma suka warware rantsuwarsu bayan ɗaukar alƙawarinsu, suka kuma soki addininku, to sai ku yaƙi shugabannin kafirci, don kuwa ba su da alƙawari, ko yin haka zai sa su daina

(13) Yanzu ba za ku yaƙi mutanen da suka warware alƙawarinsu ba, kuma (tun farko) sun yi nufin fitar da Manzo (daga Makka), su ne kuma suka fara far muku da yaƙi? Yanzu kwa riƙa tsoron su? To Allah ne Ya fi cancantar ku ji tsoron Sa idan kun kasance muminai

قَٰتِلُوهُمْ يُعَذِّبْهُمُ ٱللَّهُ بِأَيْدِيكُمْ وَيُخْزِهِمْ وَيَنصُرْكُمْ
عَلَيْهِمْ وَيَشْفِ صُدُورَ قَوْمٍ مُّؤْمِنِينَ ﴿١٤﴾ وَيُذْهِبْ غَيْظَ
قُلُوبِهِمْ ۗ وَيَتُوبُ ٱللَّهُ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿١٥﴾
أَمْ حَسِبْتُمْ أَن تُتْرَكُوا۟ وَلَمَّا يَعْلَمِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ جَٰهَدُوا۟ مِنكُمْ
وَلَمْ يَتَّخِذُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَا رَسُولِهِۦ وَلَا ٱلْمُؤْمِنِينَ وَلِيجَةً ۚ
وَٱللَّهُ خَبِيرٌۢ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿١٦﴾ مَا كَانَ لِلْمُشْرِكِينَ أَن يَعْمُرُوا۟ مَسَٰجِدَ
ٱللَّهِ شَٰهِدِينَ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِم بِٱلْكُفْرِ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ حَبِطَتْ
أَعْمَٰلُهُمْ وَفِى ٱلنَّارِ هُمْ خَٰلِدُونَ ﴿١٧﴾ إِنَّمَا يَعْمُرُ مَسَٰجِدَ
ٱللَّهِ مَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَأَقَامَ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَى
ٱلزَّكَوٰةَ وَلَمْ يَخْشَ إِلَّا ٱللَّهَ ۖ فَعَسَىٰٓ أُو۟لَٰٓئِكَ أَن يَكُونُوا۟ مِنَ
ٱلْمُهْتَدِينَ ﴿١٨﴾ ۞ أَجَعَلْتُمْ سِقَايَةَ ٱلْحَآجِّ وَعِمَارَةَ ٱلْمَسْجِدِ
ٱلْحَرَامِ كَمَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَجَٰهَدَ فِى سَبِيلِ
ٱللَّهِ ۚ لَا يَسْتَوُۥنَ عِندَ ٱللَّهِ ۗ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ
﴿١٩﴾ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَهَاجَرُوا۟ وَجَٰهَدُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمْوَٰلِهِمْ
وَأَنفُسِهِمْ أَعْظَمُ دَرَجَةً عِندَ ٱللَّهِ ۚ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْفَآئِزُونَ ﴿٢٠﴾

(14) Ku yaƙe su, Allah zai azabtar da su ta hannayenku, Ya kuma kunyatar da su, kuma Ya taimake ku a kansu, Ya kuma warkar da zukatan muminai
(15) Ya kuma tafiyar da ɓacin ransu. Allah kuma Ya karɓi tuban duk wanda Ya ga dama. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima
(16) Ko kuwa kuna tsammanin za a ƙyale ku ne (sakaka) alhali kuwa har yanzu Allah bai tantance waɗanda suka yi jihadi ba a cikinku, ba su kuma riƙi wasu masoya ba banda Allah da Manzonsa da muminai? Allah Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne
(17) Ba zai taɓa yiwuwa mushrikai su raya masallatan Allah ba, alhalin kuwa suna masu iƙirarin kafirci ga kawunansu. Waɗannan ayyukansu sun ɓaci kuma a cikin wuta za su dawwama
(18) Lalle mai raya masallatan Allah shi ne kawai wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira ya kuma tsayar da salla, kuma ya ba da zakka, bai kuma ji tsoron wani ba sai Allah. To waɗannan tabbas suna cikin shiryayyu
(19) Yanzu kwa mayar da shayar da alhazai da raya Masallaci mai alfarma kamar wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira ya kuma yi jihadi saboda Allah? Ai ba za su zama ɗaya ba a wurin Allah. Allah kuma ba Ya shiryar da mutane azzalumai
(20) Waɗanda suka yi imani kuma suka yi hijira suka yi jihadi saboda Allah da dukiyoyinsu da kawunansu su suka fi girman daraja a wurin Allah kuma waɗannan su ne marabauta

يُبَشِّرُهُمْ رَبُّهُم بِرَحْمَةٍ مِّنْهُ وَرِضْوَٰنٍ وَجَنَّٰتٍ لَّهُمْ فِيهَا
نَعِيمٌ مُّقِيمٌ ﴿٢١﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عِندَهُۥٓ أَجْرٌ
عَظِيمٌ ﴿٢٢﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَتَّخِذُوٓا۟ ءَابَآءَكُمْ
وَإِخْوَٰنَكُمْ أَوْلِيَآءَ إِنِ ٱسْتَحَبُّوا۟ ٱلْكُفْرَ عَلَى ٱلْإِيمَٰنِ ۚ
وَمَن يَتَوَلَّهُم مِّنكُمْ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٢٣﴾ قُلْ إِن
كَانَ ءَابَآؤُكُمْ وَأَبْنَآؤُكُمْ وَإِخْوَٰنُكُمْ وَأَزْوَٰجُكُمْ
وَعَشِيرَتُكُمْ وَأَمْوَٰلٌ ٱقْتَرَفْتُمُوهَا وَتِجَٰرَةٌ تَخْشَوْنَ
كَسَادَهَا وَمَسَٰكِنُ تَرْضَوْنَهَآ أَحَبَّ إِلَيْكُم مِّنَ ٱللَّهِ
وَرَسُولِهِۦ وَجِهَادٍ فِى سَبِيلِهِۦ فَتَرَبَّصُوا۟ حَتَّىٰ يَأْتِىَ ٱللَّهُ
بِأَمْرِهِۦ ۗ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْفَٰسِقِينَ ﴿٢٤﴾ لَقَدْ نَصَرَكُمُ
ٱللَّهُ فِى مَوَاطِنَ كَثِيرَةٍ وَيَوْمَ حُنَيْنٍ إِذْ أَعْجَبَتْكُمْ
كَثْرَتُكُمْ فَلَمْ تُغْنِ عَنكُمْ شَيْـًٔا وَضَاقَتْ عَلَيْكُمُ
ٱلْأَرْضُ بِمَا رَحُبَتْ ثُمَّ وَلَّيْتُم مُّدْبِرِينَ ﴿٢٥﴾ ثُمَّ أَنزَلَ ٱللَّهُ
سَكِينَتَهُۥ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَعَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ وَأَنزَلَ جُنُودًا
لَّمْ تَرَوْهَا وَعَذَّبَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ۚ وَذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٦﴾

(21) Ubangijinsu Yana yi musu albishir da rahama da yarda daga gare Shi, kana da gidajen Aljanna (waɗanda) a cikinsu suke da ni'imomi masu ɗorewa
(22) Su madawwama ne a cikinsu har abada. Lalle lada mai girma yana wurin Allah
(23) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ɗauki iyayenku da 'yan'uwanku masoya muddin dai sun fifita kafirci a kan imani. Duk kuwa waɗanda suka ɗauke su (masoya) daga cikinku to waɗannan su ne azzalumai
(24) Ka ce: "Idan iyayenku da 'ya'yanku da matanku da danginku da dukiyoyin da kuka tara da kasuwanci da kuke tsoron gurguncewarsa da kuma gidajen da kuke sha'awa; idan har su kuka fi so fiye da Allah da Manzonsa da kuma jihadi saboda Shi, to sai ku saurara har Allah Ya zo da al'amarinsa. Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane fasiƙai."
(25) Lalle haƙiƙa Allah Ya taimake ku a wurare da yawa, da kuma ranar (yaƙin) Hunaini lokacin da yawanku ya ruɗe ku sai (yawan naku) bai amfana muku komai ba, ƙasa kuma ta yi muku ƙunci duk da yalwarta, sannan kuka juya kuna masu ba da baya
(26) Sannan Allah Ya saukar wa da Manzonsa da kuma muminai nutsuwarsa, Ya kuma saukar da wasu rundunoni da ba kwa gani, Ya kuma azabtar da waɗanda suka kafirta. Wannan kuwa shi ne sakamakon kafirai

ثُمَّ يَتُوبُ ٱللَّهُ مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ عَلَىٰ مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ
غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٢٧ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّمَا ٱلۡمُشۡرِكُونَ
نَجَسٞ فَلَا يَقۡرَبُواْ ٱلۡمَسۡجِدَ ٱلۡحَرَامَ بَعۡدَ عَامِهِمۡ هَٰذَاۚ
وَإِنۡ خِفۡتُمۡ عَيۡلَةٗ فَسَوۡفَ يُغۡنِيكُمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦٓ
إِن شَآءَۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٢٨ قَٰتِلُواْ ٱلَّذِينَ
لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَلَا بِٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَلَا يُحَرِّمُونَ
مَا حَرَّمَ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَلَا يَدِينُونَ دِينَ ٱلۡحَقِّ مِنَ
ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ حَتَّىٰ يُعۡطُواْ ٱلۡجِزۡيَةَ عَن يَدٖ
وَهُمۡ صَٰغِرُونَ ٢٩ وَقَالَتِ ٱلۡيَهُودُ عُزَيۡرٌ ٱبۡنُ ٱللَّهِ
وَقَالَتِ ٱلنَّصَٰرَى ٱلۡمَسِيحُ ٱبۡنُ ٱللَّهِۖ ذَٰلِكَ قَوۡلُهُم
بِأَفۡوَٰهِهِمۡۖ يُضَٰهِـُٔونَ قَوۡلَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن قَبۡلُۚ
قَٰتَلَهُمُ ٱللَّهُۖ أَنَّىٰ يُؤۡفَكُونَ ٣٠ ٱتَّخَذُوٓاْ أَحۡبَارَهُمۡ
وَرُهۡبَٰنَهُمۡ أَرۡبَابٗا مِّن دُونِ ٱللَّهِ وَٱلۡمَسِيحَ ٱبۡنَ
مَرۡيَمَ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُوٓاْ إِلَٰهٗا وَٰحِدٗاۖ
لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ سُبۡحَٰنَهُۥ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٣١

(27) Sannan bayan wannan Allah zai karɓi tuban wanda Ya ga dama. Allah kuwa Mai gafara ne, Mai rahama
(28) Ya ku waɗanda suka yi imani, lalle mushrikai najasa ne kawai, saboda haka kada su kusanci Masallaci mai alfarma bayan wannan shekarar tasu. Idan kuma kuna tsoron talauci ne to Allah zai wadata ku daga falalarsa idan Ya ga dama. Lalle Allah Masani ne, Mai hikima
(29) Ku yaƙi waɗanda ba sa yin imani da Allah da ranar lahira, ba kuma sa haramta abin da Allah da Manzonsa suka haramta, kuma ba sa yin addini na gaskiya, daga waɗanda aka bai wa littafi har sai (sun yarda) za su ba da jizya[1] da hannunsu a ƙasƙance
(30) Yahudawa sun ce: "Uzairu ɗan Allah ne." Nasara kuma suka ce: "Almasihu ɗan Allah ne." Wannan faɗarsu ce kawai da bakunansu; suna kwaikwayon faɗar kafiran da suka gabace su ne. Allah Ya tsine musu. Ta ƙaƙa ake kautar da su daga gaskiya?
(31) Sun ɗauki malamansu da masu ibadarsu da kuma Almasihu ɗan Maryamu iyayen giji maimakon Allah[2], alhali kuwa ba abin da aka umarce su sai su bauta wa Abin bauta Ɗaya, babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. Ya tsarkaka daga abin da suke tara Shi da shi

(1) Jizya, ita ce dukiyar da ake karɓa daga hannun Yahudu da Nasara waɗanda ake zaune da su lafiya a ƙasar Musulmi,domin ɗauke mu shiga rundunar Musulmi, sannan a ba su kariya daga abokan gaba. Ba akarɓar zakka daga hannunswannan haƙƙi ne da ya shafi Musulmi kaɗai.

(2) Watau suna yi wa malamansu da masu bauta a cikinsu makauniyar biyayya, suna haramta musu halal, su kuma halatta musu haram. Nasara sun ɗauki Annabi Isa ( ) abin bauta ba Allah ba.

يُرِيدُونَ أَن يُطْفِـُٔوا۟ نُورَ ٱللَّهِ بِأَفْوَٰهِهِمْ وَيَأْبَى ٱللَّهُ إِلَّآ أَن
يُتِمَّ نُورَهُۥ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿٣٢﴾ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ
رَسُولَهُۥ بِٱلْهُدَىٰ وَدِينِ ٱلْحَقِّ لِيُظْهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ
كُلِّهِۦ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْمُشْرِكُونَ ﴿٣٣﴾ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوٓا۟ إِنَّ كَثِيرًا مِّنَ ٱلْأَحْبَارِ وَٱلرُّهْبَانِ لَيَأْكُلُونَ
أَمْوَٰلَ ٱلنَّاسِ بِٱلْبَٰطِلِ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ ۗ وَٱلَّذِينَ
يَكْنِزُونَ ٱلذَّهَبَ وَٱلْفِضَّةَ وَلَا يُنفِقُونَهَا فِى
سَبِيلِ ٱللَّهِ فَبَشِّرْهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿٣٤﴾ يَوْمَ يُحْمَىٰ عَلَيْهَا
فِى نَارِ جَهَنَّمَ فَتُكْوَىٰ بِهَا جِبَاهُهُمْ وَجُنُوبُهُمْ
وَظُهُورُهُمْ ۖ هَٰذَا مَا كَنَزْتُمْ لِأَنفُسِكُمْ فَذُوقُوا۟ مَا كُنتُمْ
تَكْنِزُونَ ﴿٣٥﴾ إِنَّ عِدَّةَ ٱلشُّهُورِ عِندَ ٱللَّهِ ٱثْنَا عَشَرَ
شَهْرًا فِى كِتَٰبِ ٱللَّهِ يَوْمَ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ مِنْهَآ
أَرْبَعَةٌ حُرُمٌ ۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلْقَيِّمُ ۚ فَلَا تَظْلِمُوا۟ فِيهِنَّ
أَنفُسَكُمْ ۚ وَقَٰتِلُوا۟ ٱلْمُشْرِكِينَ كَآفَّةً كَمَا
يُقَٰتِلُونَكُمْ كَآفَّةً ۚ وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلْمُتَّقِينَ ﴿٣٦﴾

(32) Suna nufi ne su dushashe hasken Allah da bakunansu, Allah kuwa ba zai ƙyale ba har sai Ya cika haskensa ko da kuwa kafirai sun ƙi
(33) Shi ne wanda Ya aiko Manzonsa da shiriya da kuma addini na gaskiya don Ya ɗora shi a kan dukkanin addinai, ko da kuwa mushrikai sun ƙi
(34) Ya ku waɗanda suka yi imani, lalle da yawa daga malaman (Yahudawa) da masu ibada (Nasara) tabbas suna cin dukiyoyin mutane ta hanyar cuta, suna kuma toshe hanyar Allah. Waɗanda kuma suke ɓoye zinariya da azurfa ba sa ciyar da ita saboda Allah[1], to ka yi musu albishir da wata azaba mai raɗaɗi
(35) Ranar da za a narkar da su (zinariya da azurfa) cikin wutar Jahannama sannan a yi wa fuskokinsu da kuyaɓunsu da bayansu lalas da su, (a ce da su): "Wannan shi ne abin da kuka taskace wa kanku, sai ku ɗanɗani abin da kuka kasance kuna taskacewa."
(36) Lalle adadin watanni a wurin Allah wata goma sha biyu ne a cikin littafin Allah, tun ranar da Ya halicci sammai da ƙasa, daga cikinsu akwai (wata) huɗu masu alfarma[2]. Wannan shi ne addini madaidaici. To kada ku zalunci kanku a cikinsu[3], kuma ku yaƙi mushrikai gaba ɗaya kamar yadda suke yaƙar ku gaba ɗaya. Ku kuma sani cewa Allah Yana tare da masu taƙawa

(1) Watau ba sa fitar da zakka daga dukiyarsu.

(2) Su ne watan Zulƙi'ida da Zulhijja da Al-Muharram da Rajab.

(3) Watau ta hanyar shiga yaƙi da wasu ko aikata miyagun laifuka.

إِنَّمَا ٱلنَّسِيٓءُ زِيَادَةٌ فِى ٱلْكُفْرِ ۖ يُضَلُّ بِهِ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ يُحِلُّونَهُۥ عَامًا وَيُحَرِّمُونَهُۥ عَامًا لِّيُوَاطِـُٔوا۟
عِدَّةَ مَا حَرَّمَ ٱللَّهُ فَيُحِلُّوا۟ مَا حَرَّمَ ٱللَّهُ ۚ زُيِّنَ لَهُمْ
سُوٓءُ أَعْمَـٰلِهِمْ ۗ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْكَـٰفِرِينَ
﴿٣٧﴾ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مَا لَكُمْ إِذَا قِيلَ لَكُمُ
ٱنفِرُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ٱثَّاقَلْتُمْ إِلَى ٱلْأَرْضِ ۚ أَرَضِيتُم
بِٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا مِنَ ٱلْـَٔاخِرَةِ ۚ فَمَا مَتَـٰعُ ٱلْحَيَوٰةِ
ٱلدُّنْيَا فِى ٱلْـَٔاخِرَةِ إِلَّا قَلِيلٌ ﴿٣٨﴾ إِلَّا تَنفِرُوا۟ يُعَذِّبْكُمْ
عَذَابًا أَلِيمًا وَيَسْتَبْدِلْ قَوْمًا غَيْرَكُمْ وَلَا تَضُرُّوهُ
شَيْـًٔا ۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٣٩﴾ إِلَّا تَنصُرُوهُ
فَقَدْ نَصَرَهُ ٱللَّهُ إِذْ أَخْرَجَهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ثَانِىَ ٱثْنَيْنِ
إِذْ هُمَا فِى ٱلْغَارِ إِذْ يَقُولُ لِصَـٰحِبِهِۦ لَا تَحْزَنْ إِنَّ ٱللَّهَ
مَعَنَا ۖ فَأَنزَلَ ٱللَّهُ سَكِينَتَهُۥ عَلَيْهِ وَأَيَّدَهُۥ بِجُنُودٍ
لَّمْ تَرَوْهَا وَجَعَلَ كَلِمَةَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ٱلسُّفْلَىٰ ۗ
وَكَلِمَةُ ٱللَّهِ هِىَ ٱلْعُلْيَا ۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٤٠﴾

(37) Lalle jinkiri[1] ba wani abu ba ne ban da ƙari cikin kafirci, wanda da shi (jinkirin) ake ɓatar da waɗanda suka kafirta, suna halatta shi a wata shekarar, su kuma haramta shi a wata, wai don su daidaita adadin abin da Allah Ya haramta, sai su halatta abin da Allah Ya haramta. An ƙawata musu munanan ayyukansu. Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane kafirai

(38) Ya ku waɗanda suka yi imani, me ya same ku ne idan aka ce da ku ku fita yaƙi saboda Allah sai ku yi nauyin jiki? Yanzu kun zaɓi rayuwar duniya a kan ta lahira? Ai jin daɗin rayuwar duniya abu ne ƙanƙani dangane da na lahira

(39) Idan ba za ku fita (yaƙi ba to (Allah) zai azabtar da ku da azaba mai raɗaɗi, Ya kuma canja wasu mutanen daban, ba kuwa za ku cutar da Shi da komai ba. Allah kuwa Mai iko ne a kan komai

(40) Idan ba ku taimake shi ba (watau Manzon Allah) to haƙiƙa Allah Ya taimake shi lokacin da kafirai suka fitar da shi (daga Makka), alhalin suna su biyu, lokacin da suke a cikin kogo, yayin da yake ce wa abokinsa (Abubakar): "Kada ka damu, lalle Allah yana tare da mu," sai Allah Ya saukar masa da nutsuwarsa Ya kuma ƙarfafe shi da runduna wadda ba ku gan ta ba, Ya kuma sanya kalmar waɗanda suka kafirta ta zama ƙaskantacciya. Kalmar Allah kuwa ita ce maɗaukakiya. Allah kuma Mabuwayi ne, Mai hikima

(1) Wata mummunar al'ada ce ta Larabawa a jahiiyya, sukan jinkirta watan Muharram su musanya shi da Safar, domin su halatta wa kansu yin yaƙi a cikinsa.

انفِرُوا۟ خِفَافًا وَثِقَالًا وَجَٰهِدُوا۟ بِأَمْوَٰلِكُمْ وَأَنفُسِكُمْ
فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۚ ذَٰلِكُمْ خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ
﴿٤١﴾ لَوْ كَانَ عَرَضًا قَرِيبًا وَسَفَرًا قَاصِدًا لَّٱتَّبَعُوكَ
وَلَٰكِنۢ بَعُدَتْ عَلَيْهِمُ ٱلشُّقَّةُ ۚ وَسَيَحْلِفُونَ بِٱللَّهِ
لَوِ ٱسْتَطَعْنَا لَخَرَجْنَا مَعَكُمْ يُهْلِكُونَ أَنفُسَهُمْ وَٱللَّهُ
يَعْلَمُ إِنَّهُمْ لَكَٰذِبُونَ ﴿٤٢﴾ عَفَا ٱللَّهُ عَنكَ لِمَ أَذِنتَ لَهُمْ
حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَكَ ٱلَّذِينَ صَدَقُوا۟ وَتَعْلَمَ ٱلْكَٰذِبِينَ
﴿٤٣﴾ لَا يَسْتَـْٔذِنُكَ ٱلَّذِينَ يُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ أَن
يُجَٰهِدُوا۟ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِٱلْمُتَّقِينَ ﴿٤٤﴾
إِنَّمَا يَسْتَـْٔذِنُكَ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ
وَٱرْتَابَتْ قُلُوبُهُمْ فَهُمْ فِى رَيْبِهِمْ يَتَرَدَّدُونَ ﴿٤٥﴾ * وَلَوْ
أَرَادُوا۟ ٱلْخُرُوجَ لَأَعَدُّوا۟ لَهُۥ عُدَّةً وَلَٰكِن كَرِهَ ٱللَّهُ ٱنۢبِعَاثَهُمْ
فَثَبَّطَهُمْ وَقِيلَ ٱقْعُدُوا۟ مَعَ ٱلْقَٰعِدِينَ ﴿٤٦﴾ لَوْ خَرَجُوا۟ فِيكُم
مَّا زَادُوكُمْ إِلَّا خَبَالًا وَلَأَوْضَعُوا۟ خِلَٰلَكُمْ يَبْغُونَكُمُ
ٱلْفِتْنَةَ ۖ وَفِيكُمْ سَمَّٰعُونَ لَهُمْ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٤٧﴾

(41) Ku fita yaƙi kuna da kuzari ko ba ku da shi, ku kuma yi yaƙi da dukiyoyinku da kawunanku saboda Allah. Wannan ya fi alheri a gare ku, in kun kasance kun san (haka)
(42) Da (abin da za su samu) amfani ne na kusa, ko tafiya gajeriya, to lalle da sun bi ka, sai dai kuma tafiyar ta yi musu tsawo; kuma za su zo suna rantsuwa da Allah cewa: "Da mun sami hali da lalle mun fita tare da ku[1]", suna hallaka kansu ne kawai, Allah kuwa Yana sane da cewa lalle su tabbas maƙaryata ne
(43) Allah Ya yafe maka; don me ka yi musu izini? Ai har sai ka gane musu gaskiya ka kuma san maƙaryata
(44) Waɗanda suka yi imani da Allah da ranar lahira ba sa neman izininka don kada su yi yaƙi da dukiyoyinsu da kawunansu. Allah kuwa yana sane da masu taƙawa
(45) Waɗanda kawai suke neman izininka su ne waɗanda ba sa imani da Allah da ranar lahira, zukatansu kuma suka yi kokwanto, saboda haka suke ta dawurwuri a cikin kokwantonsu
(46) Da kuwa sun yi niyyar fita to da sun yi masa tanadi, sai dai kuma Allah Ya ƙi zaburar da su, sai Ya dankwafar da su, aka kuma ce (da su): "Ku zauna tare da mazauna (gida)[2]."
(47) Lau kama (wanafiki) wangetoka (kwenda Jihadi) pamoja nanyi wasingekuzidishieni isipokuwa mchafuko (mburugano) tu, na wangekwenda mbio kati yenu wakikutilieni fitina. Na miongoni mwenu wapo (wapelelezi) wanaosikiliza sana (habari kwenu) na kuzipeleka kwao. Na Allah anawajua mno madhalimu

(1) Watau zuwa yaƙin Tabuka.

(2) Watau mata da yara da marasa lafiya da masu lalura waɗanda ba za su iya fita yaƙi ba.

لَقَدِ ٱبْتَغَوُا۟ ٱلْفِتْنَةَ مِن قَبْلُ وَقَلَّبُوا۟ لَكَ ٱلْأُمُورَ حَتَّىٰ
جَآءَ ٱلْحَقُّ وَظَهَرَ أَمْرُ ٱللَّهِ وَهُمْ كَٰرِهُونَ ﴿٤٨﴾ وَمِنْهُم
مَّن يَقُولُ ٱئْذَن لِّى وَلَا تَفْتِنِّىٓ ۚ أَلَا فِى ٱلْفِتْنَةِ سَقَطُوا۟ ۗ وَإِنَّ
جَهَنَّمَ لَمُحِيطَةٌۢ بِٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٤٩﴾ إِن تُصِبْكَ
حَسَنَةٌ تَسُؤْهُمْ ۖ وَإِن تُصِبْكَ مُصِيبَةٌ يَقُولُوا۟ قَدْ
أَخَذْنَآ أَمْرَنَا مِن قَبْلُ وَيَتَوَلَّوا۟ وَّهُمْ فَرِحُونَ ﴿٥٠﴾ قُل
لَّن يُصِيبَنَآ إِلَّا مَا كَتَبَ ٱللَّهُ لَنَا هُوَ مَوْلَىٰنَا ۚ وَعَلَى
ٱللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ ٱلْمُؤْمِنُونَ ﴿٥١﴾ قُلْ هَلْ تَرَبَّصُونَ بِنَآ إِلَّآ
إِحْدَى ٱلْحُسْنَيَيْنِ ۖ وَنَحْنُ نَتَرَبَّصُ بِكُمْ أَن يُصِيبَكُمُ ٱللَّهُ
بِعَذَابٍ مِّنْ عِندِهِۦٓ أَوْ بِأَيْدِينَا ۖ فَتَرَبَّصُوٓا۟ إِنَّا مَعَكُم
مُّتَرَبِّصُونَ ﴿٥٢﴾ قُلْ أَنفِقُوا۟ طَوْعًا أَوْ كَرْهًا لَّن يُتَقَبَّلَ
مِنكُمْ ۖ إِنَّكُمْ كُنتُمْ قَوْمًا فَٰسِقِينَ ﴿٥٣﴾ وَمَا
مَنَعَهُمْ أَن تُقْبَلَ مِنْهُمْ نَفَقَٰتُهُمْ إِلَّآ أَنَّهُمْ كَفَرُوا۟
بِٱللَّهِ وَبِرَسُولِهِۦ وَلَا يَأْتُونَ ٱلصَّلَوٰةَ إِلَّا وَهُمْ
كُسَالَىٰ وَلَا يُنفِقُونَ إِلَّا وَهُمْ كَٰرِهُونَ ﴿٥٤﴾

(48) Hakika tun da can sun nemi yada fitina, suka hargitsa maka al'amura, har sai da gaskiya ta zo, al'amarin Allah kuma ya bayyana, su kuwa suna masu kin (haka)
(49) Daga cikinsu kuma akwai wanda yake cewa: "Ka yi mani izinin (zama), kada ka jefa ni cikin fitina." Tabbas, ai cikin fitinar suka fada. Lalle Jahannama kuwa mai kewaye kafirai cei
(50) Idan wani alheri ya same ka sai ya bakanta musu rai; idan kuwa musiba ce ta same ka sai su rika cewa: "Hakika mu da ma tuni mun dauki matakin kauce mata[1]," sai kuma su juya baya suna masu farin ciki
(51) Ka ce: "Ba abin da zai same mu sai abin da Allah Ya rubuta mana, shi ne Majibincin al'amuranmu; kuma ga Allah kadai muminai sai su dogara."
(52) Ka ce: "Shin akwai abin da kuke jira ya same mu in ban da dayan kyawawan abubuwa biyu (wato nasara ko shahada). Mu kuwa muna jiran (mu ga) Allah Ya aukar muku da wata azaba daga wurinsa ko kuwa ta hannunmu? To sai ku jira, lalle mu ma masu jira ne tare da ku."
(53) Ka ce: "Ku ciyar (da dukiyarku) cikin dadin rai ko a bisa dole (duka dai suke), ba za a karba muku ba; don kuwa lalle kun kasance ku mutane ne fasikai."
(54) Ba kuwa abin da yah ana a karbi ciyarwar tasu sai don sun kafirce wa Allah da Manzonsa, ba sa kuma zuwa salla sai suna cikin kasala, ba sa kuma sa ciyarwa sai aka tilas,

(1) Watau da suka ki fita yaki tare da Manzon Allah ( ).

فَلَا تُعۡجِبۡكَ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُمۡۚ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيُعَذِّبَهُم
بِهَا فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَتَزۡهَقَ أَنفُسُهُمۡ وَهُمۡ كَٰفِرُونَ
٥٥ وَيَحۡلِفُونَ بِٱللَّهِ إِنَّهُمۡ لَمِنكُمۡ وَمَا هُم مِّنكُمۡ وَلَٰكِنَّهُمۡ
قَوۡمٞ يَفۡرَقُونَ ٥٦ لَوۡ يَجِدُونَ مَلۡجَـًٔا أَوۡ مَغَٰرَٰتٍ أَوۡ مُدَّخَلٗا
لَّوَلَّوۡاْ إِلَيۡهِ وَهُمۡ يَجۡمَحُونَ ٥٧ وَمِنۡهُم مَّن يَلۡمِزُكَ فِي
ٱلصَّدَقَٰتِ فَإِنۡ أُعۡطُواْ مِنۡهَا رَضُواْ وَإِن لَّمۡ يُعۡطَوۡاْ مِنۡهَآ إِذَا
هُمۡ يَسۡخَطُونَ ٥٨ وَلَوۡ أَنَّهُمۡ رَضُواْ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ
وَقَالُواْ حَسۡبُنَا ٱللَّهُ سَيُؤۡتِينَا ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦ وَرَسُولُهُۥٓ
إِنَّآ إِلَى ٱللَّهِ رَٰغِبُونَ ٥٩ ۞ إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلۡفُقَرَآءِ وَٱلۡمَسَٰكِينِ
وَٱلۡعَٰمِلِينَ عَلَيۡهَا وَٱلۡمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمۡ وَفِي ٱلرِّقَابِ
وَٱلۡغَٰرِمِينَ وَفِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِۖ فَرِيضَةٗ
مِّنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٦٠ وَمِنۡهُمُ ٱلَّذِينَ يُؤۡذُونَ
ٱلنَّبِيَّ وَيَقُولُونَ هُوَ أُذُنٞۚ قُلۡ أُذُنُ خَيۡرٖ لَّكُمۡ يُؤۡمِنُ
بِٱللَّهِ وَيُؤۡمِنُ لِلۡمُؤۡمِنِينَ وَرَحۡمَةٞ لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ
مِنكُمۡۚ وَٱلَّذِينَ يُؤۡذُونَ رَسُولَ ٱللَّهِ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٦١

(55) To kada dukiyoyinsu da ‘ya’yansu su ƙayatar da kai. Allah Yana nufin kawai Ya azabta su ne da su a rayuwar duniya, rayukansu kuma su zazzago a halin suna kafirai
(56) Sukan kuma rantse da Allah cewa lalle suna tare da ku, alhali kuwa ba sa tare da ku, kawai dai su wasu mutane ne matsorata
(57) Da za su sami wata mafaka ko wani kogo ko wata mashiga, to da sun juya zuwa gare shi suna gaggawar (shiga)
(58) Daga cikinsu kuma akwai waɗanda suke aibata ka game da rabon sadaka; idan an ba su wani abu daga cikinta to sai su gamsu, idan kuwa ba a ba su daga cikinta ba sai ka gan su suna fushi
(59) Da kuwa za su yarda da abin da Allah da Manzonsa suka ba su, su kuma ce: “Allah ya ishe mu, kuma Allah zai ba mu daga falalarsa Manzonsa ma (zai ba mu), lalle mu masu kwaɗayi ne a wurin Allah kaɗai.”
(60) Dukiyoyin zakka na matalauta ne kaɗai da miskinai da ma’aikatanta[1] da waɗanda ake lallashin zukatansu da kuma game da ‘yanta bayi da waɗanda ake bi bashi da kuma wajen jihadi saboda Allah da matafiyi. Farilla ce daga Allah. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima
(61) Daga cikinsu kuma akwai waɗanda suke cutar Annabi suna kuma cewa: “Shi mai saurare ne kawai[2].” Ka ce (da su: Shi) “Mai sauraren alheri ne dominku; yana imani da Allah, yana kuma gaskata muminai, kuma rahama ne ga waɗanda suka yi imani daga cikinku.” Waɗanda kuwa suke cutar Manzon Allah suna da azaba mai raɗaɗi

(1) Su ne waɗanda aka wakilta wajen karɓo ta da kula da ita da rarraba wa mabuƙata.

(2) Wai shi mai ɗaukar maganganu ne kawai yana yarda da su ba tare da ya tantance gaskiyarsu da rashinta ba.

يَحۡلِفُونَ بِٱللَّهِ لَكُمۡ لِيُرۡضُوكُمۡ وَٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ أَحَقُّ
أَن يُرۡضُوهُ إِن كَانُواْ مُؤۡمِنِينَ ٦٢ أَلَمۡ يَعۡلَمُوٓاْ أَنَّهُۥ مَن
يُحَادِدِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَأَنَّ لَهُۥ نَارَ جَهَنَّمَ خَٰلِدٗا فِيهَاۚ
ذَٰلِكَ ٱلۡخِزۡيُ ٱلۡعَظِيمُ ٦٣ يَحۡذَرُ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ أَن
تُنَزَّلَ عَلَيۡهِمۡ سُورَةٞ تُنَبِّئُهُم بِمَا فِي قُلُوبِهِمۡۚ قُلِ ٱسۡتَهۡزِءُواْ
إِنَّ ٱللَّهَ مُخۡرِجٞ مَّا تَحۡذَرُونَ ٦٤ وَلَئِن سَأَلۡتَهُمۡ
لَيَقُولُنَّ إِنَّمَا كُنَّا نَخُوضُ وَنَلۡعَبُۚ قُلۡ أَبِٱللَّهِ وَءَايَٰتِهِۦ
وَرَسُولِهِۦ كُنتُمۡ تَسۡتَهۡزِءُونَ ٦٥ لَا تَعۡتَذِرُواْ قَدۡ كَفَرۡتُم
بَعۡدَ إِيمَٰنِكُمۡۚ إِن نَّعۡفُ عَن طَآئِفَةٖ مِّنكُمۡ نُعَذِّبۡ طَآئِفَةَۢ
بِأَنَّهُمۡ كَانُواْ مُجۡرِمِينَ ٦٦ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ وَٱلۡمُنَٰفِقَٰتُ
بَعۡضُهُم مِّنۢ بَعۡضٖۘ يَأۡمُرُونَ بِٱلۡمُنكَرِ وَيَنۡهَوۡنَ
عَنِ ٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَقۡبِضُونَ أَيۡدِيَهُمۡۚ نَسُواْ ٱللَّهَ فَنَسِيَهُمۡۚ
إِنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ هُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ ٦٧ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ
وَٱلۡمُنَٰفِقَٰتِ وَٱلۡكُفَّارَ نَارَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ هِيَ
حَسۡبُهُمۡۚ وَلَعَنَهُمُ ٱللَّهُۖ وَلَهُمۡ عَذَابٞ مُّقِيمٞ ٦٨

(62) Suna rantse muku da Allah don su samu yardarku, Allah da Manzonsa kuwa su suka fi cancanta su yardar da su in sun kasance muminai
(63) Yanzu ba su sani ba cewa, wanda yake jayayya da Allah da Manzonsa, to lalle yana da wutar Jahannama da zai dawwama a cikinta? Wannan kuwa kunyata ce mai girma
(64) Munafukai suna tsoron a saukar musu da wata sura mai ba su labarin abin da yake cikin zukatansu. Ka ce: "Ku yi ta izgili, lalle Allah Mai bayyana abin da kuke tsoron (bayyanarsa) ne."
(65) Kuma lalle idan har ka tambaye su, tabbas za su ce: "Kawai muna kutse ne da wasa." To ka ce (da su): "Yanzu Allah ne da ayoyinsa da Manzonsa kuka kasance kuna yi wa izgili?"
(66) Kada ku kawo wani uziri, hakika kun dai kafirta bayan imaninku. Idan Muka yafe wa wata kungiya daga cikinku to za Mu azabtar da wata kungiyar saboda kuwa sun kasance masu laifi ne
(67) Munafukai maza da munafukai mata sun yi kama da juna (wajen munafunci). Suna umurni da mummunan aiki suna kuma hana kyakkyawan aiki, kuma suna damke hannayensu (wajen yin alheri); sun manta da Allah, sai Shi ma Ya yi watsi da su. Lalle munafikai su ne fasikai
(68) Allah kuwa Ya yi wa munafukai maza da mata da kuma kafirai alkawarin wutar Jahannama wadda za su dawwama a cikinta. Ita ta ishe su. Allah kuma Ya tsine musu, suna kuma da azaba mai dorewa

كَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ كَانُوٓاْ أَشَدَّ مِنكُمۡ قُوَّةٗ وَأَكۡثَرَ أَمۡوَٰلٗا
وَأَوۡلَٰدٗا فَٱسۡتَمۡتَعُواْ بِخَلَٰقِهِمۡ فَٱسۡتَمۡتَعۡتُم بِخَلَٰقِكُمۡ
كَمَا ٱسۡتَمۡتَعَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُم بِخَلَٰقِهِمۡ وَخُضۡتُمۡ
كَٱلَّذِي خَاضُوٓاْۚ أُوْلَٰٓئِكَ حَبِطَتۡ أَعۡمَٰلُهُمۡ فِي ٱلدُّنۡيَا
وَٱلۡأٓخِرَةِۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٦٩ أَلَمۡ يَأۡتِهِمۡ
نَبَأُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ قَوۡمِ نُوحٖ وَعَادٖ وَثَمُودَ وَقَوۡمِ
إِبۡرَٰهِيمَ وَأَصۡحَٰبِ مَدۡيَنَ وَٱلۡمُؤۡتَفِكَٰتِۚ أَتَتۡهُمۡ رُسُلُهُم
بِٱلۡبَيِّنَٰتِۖ فَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظۡلِمَهُمۡ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ
أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ٧٠ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتُ بَعۡضُهُمۡ
أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٖۚ يَأۡمُرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ
وَيُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَيُطِيعُونَ ٱللَّهَ
وَرَسُولَهُۥٓۚ أُوْلَٰٓئِكَ سَيَرۡحَمُهُمُ ٱللَّهُۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٞ
٧١ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا
ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَمَسَٰكِنَ طَيِّبَةٗ فِي جَنَّٰتِ عَدۡنٖۚ
وَرِضۡوَٰنٞ مِّنَ ٱللَّهِ أَكۡبَرُۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ٧٢

(69) (Kun yi) kama da waɗanda suke gabaninku; sun fi ku ƙarfi da yawan dukiyoyi da kuma ’ya’ya; sai suka more rabonsu (na duniya), to ku ma sai kuka more da naku rabon, kamar yadda waɗanda suke gabaninku suka more da irin nasu rabon, kuka kuma kutsa (cikin ɓarna) kamar yadda suka kutsa. Waɗannan, ayyukansu sun ruguje a duniya da lahira. Waɗannan kuwa su ne hasararru

(70) Yanzu labarin waɗanda suke gabaninsu bai zo musu ba: Mutanen (Annabi) Nuhu da Adawa da Samudawa, da mutanen (Annabi) Ibrahimu da kuma mutanen Madyana da waɗanda aka kifar (watau mutanen Annabi Luɗu)? Manzanninsu sun zo musu da (ayoyi) mabayyana; ba kuma zai zamana Allah Ya zalunce su ba sai dai kawunansu ne kawai suke zalunta

(71) Muminai maza da muninai mata kuwa masoyan juna ne: Suna yin umurni da kyakkyawan abu suna kuma hana mummunan, suna kuma tsai da salla suna ba da zakka suna kuma bin Allah da Manzonsa. Waɗannan Allah zai yi musu rahama. Lalle Allah kuwa Mabuwayi ne Mai hikima

(72) Allah Ya yi wa muninai maza da muminai mata alƙawarin gidajen Aljanna da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu suna masu dawwama a cikinsu, da kuma wuraren zama masu kyau a cikin gidajen Aljanna na dawwama. Yardar Allah kuwa ita ce fiye da komai. Wannan shi ne rabo mai girma

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ جَٰهِدِ ٱلْكُفَّارَ وَٱلْمُنَٰفِقِينَ وَٱغْلُظْ عَلَيْهِمْ ۚ
وَمَأْوَىٰهُمْ جَهَنَّمُ ۖ وَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ﴿٧٣﴾ يَحْلِفُونَ بِٱللَّهِ مَا قَالُوا۟
وَلَقَدْ قَالُوا۟ كَلِمَةَ ٱلْكُفْرِ وَكَفَرُوا۟ بَعْدَ إِسْلَٰمِهِمْ وَهَمُّوا۟
بِمَا لَمْ يَنَالُوا۟ ۚ وَمَا نَقَمُوٓا۟ إِلَّآ أَنْ أَغْنَىٰهُمُ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ
مِن فَضْلِهِۦ ۚ فَإِن يَتُوبُوا۟ يَكُ خَيْرًا لَّهُمْ ۖ وَإِن يَتَوَلَّوْا۟ يُعَذِّبْهُمُ
ٱللَّهُ عَذَابًا أَلِيمًا فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ ۚ وَمَا لَهُمْ فِى ٱلْأَرْضِ
مِن وَلِىٍّ وَلَا نَصِيرٍ ﴿٧٤﴾ * وَمِنْهُم مَّنْ عَٰهَدَ ٱللَّهَ لَئِنْ ءَاتَىٰنَا
مِن فَضْلِهِۦ لَنَصَّدَّقَنَّ وَلَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ
﴿٧٥﴾ فَلَمَّآ ءَاتَىٰهُم مِّن فَضْلِهِۦ بَخِلُوا۟ بِهِۦ وَتَوَلَّوا۟ وَّهُم
مُّعْرِضُونَ ﴿٧٦﴾ فَأَعْقَبَهُمْ نِفَاقًا فِى قُلُوبِهِمْ إِلَىٰ يَوْمِ يَلْقَوْنَهُۥ
بِمَآ أَخْلَفُوا۟ ٱللَّهَ مَا وَعَدُوهُ وَبِمَا كَانُوا۟ يَكْذِبُونَ ﴿٧٧﴾
أَلَمْ يَعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ سِرَّهُمْ وَنَجْوَىٰهُمْ وَأَنَّ ٱللَّهَ
عَلَّٰمُ ٱلْغُيُوبِ ﴿٧٨﴾ ٱلَّذِينَ يَلْمِزُونَ ٱلْمُطَّوِّعِينَ مِنَ
ٱلْمُؤْمِنِينَ فِى ٱلصَّدَقَٰتِ وَٱلَّذِينَ لَا يَجِدُونَ إِلَّا جُهْدَهُمْ
فَيَسْخَرُونَ مِنْهُمْ سَخِرَ ٱللَّهُ مِنْهُمْ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٧٩﴾

(73) Ya kai wannan Annabi, ka yaƙi kafirai da munafukai ka kuma tsananta musu. Jahannama ce kuma makomarsu. Makoma kuwa ta munana

(74) Suna rantsewa da Allah kan ba su faɗi (komai) ba, alhali kuwa tabbas sun faɗi kalmar kafirci, suka kuma kafirta bayan musuluntarsu, suka kuma yi ƙudirin aikata abin da ba su samu (dama) ba[1]; ba kuwa abin da suke jin haushi sai kawai don Allah da Manzonsa sun wadata su daga falalarsa. To idan suka tuba zai fi musu alheri; idan kuwa suka juya baya to Allah zai azabtar da su azaba mai raɗaɗi a duniya da lahira; ba su da kuwa wani majiɓincin lamari ko wani mataimaki a bayan ƙasa

(75) Daga cikinsu kuma akwai waɗanda suka yi wa Allah alƙawarin cewa: "Idan Ya arzuta mu daga falalarsa, to lalle tabbas za mu riƙa ba da sadaka, kuma lalle tabbas za mu zama cikin mutane salihai."

(76) To lokacin da Ya arzuta su ɗin sai suka yi rowa da ita (sadakar) suka kuma ba da baya suna masu bijirewa

(77) Sai Ya gadar musu da munafunci a cikin zukatansu har zuwa ranar da za su gamu da Shi, saboda saɓa wa alƙawarin da suka yi wa Allah da kuma ƙaryatawar da suka zamanto suna yi

(78) Yanzu ba su sani ba cewa, lalle Allah Ya san asirinsu da kuma ganawar da suke yi, lalle kuma Allah Shi ne cikakken Masanin gaibu?

(79) Waɗanda kuma suke aibata muminai masu yin sadaka (mai yawa) don neman lada da kuma waɗanda ba su da abin da za su bayar sai (kaɗan) gwargwadon wahalarsu, sannan su riƙa yi musu izgili, to Allah zai mayar musu da sakamakon izgilinsu, suna kuma da azaba mai raɗaɗi

(1) Watau mugun shirinsu na kashe Annabi ( ) lokacin da yake komawa Madina daga yaƙin Tabuka.

أَسْتَغْفِرْ لَهُمْ أَوْ لَا تَسْتَغْفِرْ لَهُمْ إِن تَسْتَغْفِرْ لَهُمْ سَبْعِينَ مَرَّةً
فَلَن يَغْفِرَ ٱللَّهُ لَهُمْ ۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ كَفَرُوا۟ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ۗ
وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْفَٰسِقِينَ ﴿٨٠﴾ فَرِحَ ٱلْمُخَلَّفُونَ بِمَقْعَدِهِمْ
خِلَٰفَ رَسُولِ ٱللَّهِ وَكَرِهُوٓا۟ أَن يُجَٰهِدُوا۟ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ
فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَقَالُوا۟ لَا تَنفِرُوا۟ فِى ٱلْحَرِّ ۗ قُلْ نَارُ جَهَنَّمَ أَشَدُّ حَرًّا ۚ
لَّوْ كَانُوا۟ يَفْقَهُونَ ﴿٨١﴾ فَلْيَضْحَكُوا۟ قَلِيلًا وَلْيَبْكُوا۟ كَثِيرًا جَزَآءًۢ
بِمَا كَانُوا۟ يَكْسِبُونَ ﴿٨٢﴾ فَإِن رَّجَعَكَ ٱللَّهُ إِلَىٰ طَآئِفَةٍ
مِّنْهُمْ فَٱسْتَـْٔذَنُوكَ لِلْخُرُوجِ فَقُل لَّن تَخْرُجُوا۟ مَعِىَ أَبَدًا وَلَن
تُقَٰتِلُوا۟ مَعِىَ عَدُوًّا ۖ إِنَّكُمْ رَضِيتُم بِٱلْقُعُودِ أَوَّلَ مَرَّةٍ فَٱقْعُدُوا۟
مَعَ ٱلْخَٰلِفِينَ ﴿٨٣﴾ وَلَا تُصَلِّ عَلَىٰٓ أَحَدٍ مِّنْهُم مَّاتَ أَبَدًا وَلَا تَقُمْ
عَلَىٰ قَبْرِهِۦٓ ۖ إِنَّهُمْ كَفَرُوا۟ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَمَاتُوا۟ وَهُمْ فَٰسِقُونَ
﴿٨٤﴾ وَلَا تُعْجِبْكَ أَمْوَٰلُهُمْ وَأَوْلَٰدُهُمْ ۚ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ أَن يُعَذِّبَهُم
بِهَا فِى ٱلدُّنْيَا وَتَزْهَقَ أَنفُسُهُمْ وَهُمْ كَٰفِرُونَ ﴿٨٥﴾ وَإِذَآ
أُنزِلَتْ سُورَةٌ أَنْ ءَامِنُوا۟ بِٱللَّهِ وَجَٰهِدُوا۟ مَعَ رَسُولِهِ ٱسْتَـْٔذَنَكَ
أُو۟لُوا۟ ٱلطَّوْلِ مِنْهُمْ وَقَالُوا۟ ذَرْنَا نَكُن مَّعَ ٱلْقَٰعِدِينَ ﴿٨٦﴾

(80) Ko ka nema musu gafara ko ba ka nema musu gafara ba (duk ɗaya ne). In da za ka nema musu gafara sau saba'in to Allah ba zai gafarta musu ba. Wannan kuwa saboda sun kafirce wa Allah da Manzonsa. Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane fasiƙai

(81) (Munafukai) waɗanda suka ƙi fita (yaƙi) sun yi farin ciki da zamansu (a gida) suna masu saɓa wa Manzon Allah, suka kuma ƙi su yi yaƙi da dukiyoyinsu da kawunansu saboda Allah, suka kuma ce (da junansu): "Kada ku fita yaƙi cikin zafin nan." Ka ce da su: "Wutar Jahannama ta fi tsananin zafi." Da sun zamanto suna ganewa

(82) Sai su yi dariya kaɗan su kuma yi kuka mai yawa a sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa

(83) To idan Allah Ya dawo da kai zuwa ga wata jama'a daga cikinsu sai suka nemi izinin fita a wajenka, to sai ka ce (da su): "Ba za ku fita tare da ni ba har abada, kuma ba za ku yaƙi wani abokin gaba ba tare da ni ba har abada. Lalle kun yarda da zama tun farko, to sai ku zauna tare da masu zama." (wato mata da yara)

(84) Kada ka ƙara yi wa ɗaya daga cikinsu da ya mutu salla har abada, kada kuma ka tsaya a kan ƙabarinsa (don addu'a). Lalle su sun kafirce wa Allah da Manzonsa, suka kuma mutu suna fasiƙai

(85) Kada kuma dukiyoyinsu da 'ya'yansu su ƙayatar da kai. Lalle kawai Allah Yana nufin azabtar da su ne da su (dukiyoyin da 'ya'yan), rayukansu kuma su zazzago suna kafirai

(86) Idan kuma aka saukar da wata sura mai cewa: "Ku yi imani da Allah kuma ku yi yaƙi tare da Manzonsa," sai masu wadata daga cikinsu su nemi izininka su ce: "Kyale mu mu kasance tare da masu zama (a gida, wato mata da yara)."

رَضُوا۟ بِأَن يَكُونُوا۟ مَعَ ٱلْخَوَالِفِ وَطُبِعَ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ فَهُمْ
لَا يَفْقَهُونَ ﴿٨٧﴾ لَٰكِنِ ٱلرَّسُولُ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مَعَهُۥ
جَٰهَدُوا۟ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ ۚ وَأُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلْخَيْرَٰتُ ۖ
وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ﴿٨٨﴾ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُمْ جَنَّٰتٍ تَجْرِى
مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۚ ذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿٨٩﴾
وَجَآءَ ٱلْمُعَذِّرُونَ مِنَ ٱلْأَعْرَابِ لِيُؤْذَنَ لَهُمْ وَقَعَدَ ٱلَّذِينَ
كَذَبُوا۟ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ ۚ سَيُصِيبُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنْهُمْ عَذَابٌ
أَلِيمٌ ﴿٩٠﴾ لَّيْسَ عَلَى ٱلضُّعَفَآءِ وَلَا عَلَى ٱلْمَرْضَىٰ وَلَا عَلَى ٱلَّذِينَ
لَا يَجِدُونَ مَا يُنفِقُونَ حَرَجٌ إِذَا نَصَحُوا۟ لِلَّهِ وَرَسُولِهِۦ ۚ
مَا عَلَى ٱلْمُحْسِنِينَ مِن سَبِيلٍ ۚ وَٱللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٩١﴾
وَلَا عَلَى ٱلَّذِينَ إِذَا مَآ أَتَوْكَ لِتَحْمِلَهُمْ قُلْتَ لَآ أَجِدُ
مَآ أَحْمِلُكُمْ عَلَيْهِ تَوَلَّوا۟ وَّأَعْيُنُهُمْ تَفِيضُ مِنَ ٱلدَّمْعِ
حَزَنًا أَلَّا يَجِدُوا۟ مَا يُنفِقُونَ ﴿٩٢﴾ ۞ إِنَّمَا ٱلسَّبِيلُ عَلَى
ٱلَّذِينَ يَسْتَـْٔذِنُونَكَ وَهُمْ أَغْنِيَآءُ ۚ رَضُوا۟ بِأَن يَكُونُوا۟
مَعَ ٱلْخَوَالِفِ وَطَبَعَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ فَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٩٣﴾

(87) Sun yarda da su kasance tare da mata masu zaman gida, an kuma doɗe zukatansu, saboda haka ba sa ganewa
(88) Sai dai shi Manzo da waɗanda suka yi imani tare da shi sun yi yaƙi da dukiyoyinsu da kuma kawunansu. Waɗannan kuwa suna da alherai; kuma waɗannan su ne marabauta
(89) Allah Ya tanadar musu da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu. Wannan shi ne rabo mai girma
(90) Masu kawo uzurin ƙarya daga mutanen ƙauye kuma suka zo don a yi musu izini, sai kuma waɗanda suka yi wa Allah da Manzonsa ƙarya suka yi zamansu (ba tare da kawo hanzari ba). To azaba mai raɗaɗi za ta samu waɗanda suka kafirta daga cikinsu
(91) Babu wani laifi a kan raunana ko marasa lafiya ko kuma waɗanda ba su samu abin da za su ciyar ba (don talauci), matuƙar dai sun tsarkake zuciyarsu ga Allah da Manzonsa. Babu wata hanya (ta ɗora laifi) ga masu kyautatawa. Allah kuwa Mai gafara ne, Mai jin ƙai
(92) Haka kuma babu (laifi) a kan waɗanda idan sun zo maka don ka ba su abin hawa sai ka ce: "Ba ni da abin hawan da zan ba ku," sai suka juya idanuwansu suna kwararar da hawaye don baƙin cikin ba su sami abin da za su ciyar ba
(93) Zargi kawai yana kan waɗanda suke neman izininka alhali kuwa suna mawadata. Sun yarda da su kasance tare da masu zaman gida (mata da yara). Allah kuma Ya doɗe zukatansu, saboda haka ba sa sanin (gaskiya)

يَعْتَذِرُونَ إِلَيْكُمْ إِذَا رَجَعْتُمْ إِلَيْهِمْ ۚ قُل لَّا تَعْتَذِرُوا۟
لَن نُّؤْمِنَ لَكُمْ قَدْ نَبَّأَنَا ٱللَّهُ مِنْ أَخْبَارِكُمْ ۚ وَسَيَرَى
ٱللَّهُ عَمَلَكُمْ وَرَسُولُهُۥ ثُمَّ تُرَدُّونَ إِلَىٰ عَٰلِمِ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٩٤﴾ سَيَحْلِفُونَ بِٱللَّهِ
لَكُمْ إِذَا ٱنقَلَبْتُمْ إِلَيْهِمْ لِتُعْرِضُوا۟ عَنْهُمْ ۖ فَأَعْرِضُوا۟
عَنْهُمْ ۖ إِنَّهُمْ رِجْسٌ ۖ وَمَأْوَىٰهُمْ جَهَنَّمُ جَزَآءًۢ بِمَا كَانُوا۟
يَكْسِبُونَ ﴿٩٥﴾ يَحْلِفُونَ لَكُمْ لِتَرْضَوْا۟ عَنْهُمْ ۖ فَإِن
تَرْضَوْا۟ عَنْهُمْ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يَرْضَىٰ عَنِ ٱلْقَوْمِ ٱلْفَٰسِقِينَ
﴿٩٦﴾ ٱلْأَعْرَابُ أَشَدُّ كُفْرًا وَنِفَاقًا وَأَجْدَرُ أَلَّا يَعْلَمُوا۟ حُدُودَ
مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿٩٧﴾ وَمِنَ
ٱلْأَعْرَابِ مَن يَتَّخِذُ مَا يُنفِقُ مَغْرَمًا وَيَتَرَبَّصُ بِكُمُ
ٱلدَّوَآئِرَ ۚ عَلَيْهِمْ دَآئِرَةُ ٱلسَّوْءِ ۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٩٨﴾ وَمِنَ
ٱلْأَعْرَابِ مَن يُؤْمِنُ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَيَتَّخِذُ مَا يُنفِقُ
قُرُبَٰتٍ عِندَ ٱللَّهِ وَصَلَوَٰتِ ٱلرَّسُولِ ۚ أَلَآ إِنَّهَا قُرْبَةٌ لَّهُمْ ۚ
سَيُدْخِلُهُمُ ٱللَّهُ فِى رَحْمَتِهِۦٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٩٩﴾

(94) Za su kawo muku uzurinsu idan kuka dawo musu. Ka ce: “Kada ku kawo wani uziri, mu ba za mu gaskata ku ba har abada, haƙiƙa Allah Ya faɗa mana labarinku. Allah kuwa zai ga ayyukanku Shi da Manzonsa, sannan a komar da ku zuwa ga Masanin abin da yake ɓoye da na sarari, sai Ya ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa.”
(95) Za su rantse muku da Allah idan kuka dawo wurinsu don ku ƙyale su. To ku ƙyale su ɗin. Lalle su najasa ne; makomarsu kuma wutar Jahannama ce sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa
(96) Suna rantse muku don ku yarda da su; to idan ma kun yarda da su ɗin, lalle (Shi) Allah ba zai yarda da mutane fasiƙai ba
(97) Mutanen ƙauye sun fi tsananin kafirci da munafunci, kuma su suka fi dacewa da rashin sanin dokokin da Allah Ya saukar wa Manzonsa. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima
(98) Daga mutanen ƙauye kuma akwai waɗanda suke ɗaukar abin da suke ciyarwa tara ne, suke kuma jiran faruwar masifu gare ku. To mummunar musiba ta tabbata a kansu. Allah kuma Mai ji ne, Masani
(99) Daga mutanen ƙauye ɗin kuma akwai waɗanda suke yin imani da Allah da ranar lahira, suke kuma ɗaukar abin da suke ciyarwa (hanyoyi ne) na samun kusanci ga Allah da kuma addu’o’in Manzo. Lalle wannan ibada ce gare su. Allah zai shigar da su cikin rahamarsa. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلْأَوَّلُونَ مِنَ ٱلْمُهَٰجِرِينَ وَٱلْأَنصَارِ وَٱلَّذِينَ
ٱتَّبَعُوهُم بِإِحْسَٰنٍ رَّضِىَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ وَأَعَدَّ
لَهُمْ جَنَّٰتٍ تَجْرِى تَحْتَهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا
ذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿١٠٠﴾ وَمِمَّنْ حَوْلَكُم مِّنَ ٱلْأَعْرَابِ
مُنَٰفِقُونَ ۖ وَمِنْ أَهْلِ ٱلْمَدِينَةِ مَرَدُوا۟ عَلَى ٱلنِّفَاقِ لَا تَعْلَمُهُمْ ۖ
نَحْنُ نَعْلَمُهُمْ ۚ سَنُعَذِّبُهُم مَّرَّتَيْنِ ثُمَّ يُرَدُّونَ إِلَىٰ عَذَابٍ
عَظِيمٍ ﴿١٠١﴾ وَءَاخَرُونَ ٱعْتَرَفُوا۟ بِذُنُوبِهِمْ خَلَطُوا۟ عَمَلًا صَٰلِحًا
وَءَاخَرَ سَيِّئًا عَسَى ٱللَّهُ أَن يَتُوبَ عَلَيْهِمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ
﴿١٠٢﴾ خُذْ مِنْ أَمْوَٰلِهِمْ صَدَقَةً تُطَهِّرُهُمْ وَتُزَكِّيهِم بِهَا وَصَلِّ عَلَيْهِمْ ۖ
إِنَّ صَلَوٰتَكَ سَكَنٌ لَّهُمْ ۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿١٠٣﴾ أَلَمْ يَعْلَمُوٓا۟ أَنَّ
ٱللَّهَ هُوَ يَقْبَلُ ٱلتَّوْبَةَ عَنْ عِبَادِهِۦ وَيَأْخُذُ ٱلصَّدَقَٰتِ وَأَنَّ
ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٠٤﴾ وَقُلِ ٱعْمَلُوا۟ فَسَيَرَى ٱللَّهُ عَمَلَكُمْ
وَرَسُولُهُۥ وَٱلْمُؤْمِنُونَ ۖ وَسَتُرَدُّونَ إِلَىٰ عَٰلِمِ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿١٠٥﴾ وَءَاخَرُونَ مُرْجَوْنَ لِأَمْرِ ٱللَّهِ
إِمَّا يُعَذِّبُهُمْ وَإِمَّا يَتُوبُ عَلَيْهِمْ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿١٠٦﴾

(100) Magabata kuwa na farko daga cikin masu hijira da Ansaru(1) da kuma waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa, (duka) Allah Ya yarda da su, su ma sun yarda da Shi, Ya kuma tanadar musu gidajen Aljanna da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna madawwama a cikinsu har abada. Wannan shi ne rabo mai girma

(101) Kuma daga mutanen ƙauye waɗanda suke kewaye da ku akwai munafukai, haka kuma daga mutan Madina; sun ƙware a kan munafunci, kai ba ka san su ba; Mu ne Muka san su. Za Mu azabtar da su sau biyu, sannan a komar da su zuwa ga azaba mai girma

(102) Wasu kuwa sun yi iƙirari da laifinsu, sun gauraya kyakkyawan aiki da wani mummuna, to tabbas Allah zai karɓi tubansu. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(103) CKa karɓi sadaka daga dukiyoyinsu da za ka tsarkake su kuma ka gyara musu halaye da ita, ka kuma yi musu addu'a. Lalle addu'arka nutsuwa ce a gare su. Allah kuwa Mai ji ne, Masani

(104) Shin yanzu ba su sani ba ne cewa Allah Shi Yake karɓar tuba daga bayinsa Yake kuma karɓar sadakoki, kuma lalle Shi ne Mai yawan karɓar tuba, Mai jin ƙai?

(105) Ka kuma ce: "Ku yi aiki, Allah ne zai ga aikinku shi da Manzonsa da kuma muminai, kuma za a mayar da ku zuwa ga Masanin abin da yake ɓoye da na sarari, sannan Ya ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa

(106) Wasu kuwa an jinkirta lamarinsu ne ga hukuncin Allah, ko dai ya azabtar da su ko kuma Ya karɓi tubarsu. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima

(1) Masu hijira su ne Musulmin da suka yiwo hijira daga Makka zuwa Madina. Ansaru kuwa su ne mutanen Madina waɗandasuka karɓi baƙuncin mutanen Makka, suka ba su matsugunnai.

وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُوا۟ مَسْجِدًا ضِرَارًا وَكُفْرًا وَتَفْرِيقًۢا بَيْنَ
ٱلْمُؤْمِنِينَ وَإِرْصَادًا لِّمَنْ حَارَبَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ مِن قَبْلُ ۚ
وَلَيَحْلِفُنَّ إِنْ أَرَدْنَآ إِلَّا ٱلْحُسْنَىٰ ۖ وَٱللَّهُ يَشْهَدُ إِنَّهُمْ
لَكَٰذِبُونَ ﴿١٠٧﴾ لَا تَقُمْ فِيهِ أَبَدًا ۚ لَّمَسْجِدٌ أُسِّسَ عَلَى ٱلتَّقْوَىٰ
مِنْ أَوَّلِ يَوْمٍ أَحَقُّ أَن تَقُومَ فِيهِ ۚ فِيهِ رِجَالٌ يُحِبُّونَ أَن
يَتَطَهَّرُوا۟ ۚ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلْمُطَّهِّرِينَ ﴿١٠٨﴾ أَفَمَنْ أَسَّسَ بُنْيَٰنَهُۥ
عَلَىٰ تَقْوَىٰ مِنَ ٱللَّهِ وَرِضْوَٰنٍ خَيْرٌ أَم مَّنْ أَسَّسَ بُنْيَٰنَهُۥ
عَلَىٰ شَفَا جُرُفٍ هَارٍ فَٱنْهَارَ بِهِۦ فِى نَارِ جَهَنَّمَ ۗ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى
ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٠٩﴾ لَا يَزَالُ بُنْيَٰنُهُمُ ٱلَّذِى بَنَوْا۟ رِيبَةً
فِى قُلُوبِهِمْ إِلَّآ أَن تَقَطَّعَ قُلُوبُهُمْ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ
﴿١١٠﴾ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ ٱشْتَرَىٰ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ أَنفُسَهُمْ وَأَمْوَٰلَهُم
بِأَنَّ لَهُمُ ٱلْجَنَّةَ ۚ يُقَٰتِلُونَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ فَيَقْتُلُونَ
وَيُقْتَلُونَ ۖ وَعْدًا عَلَيْهِ حَقًّا فِى ٱلتَّوْرَىٰةِ وَٱلْإِنجِيلِ
وَٱلْقُرْءَانِ ۚ وَمَنْ أَوْفَىٰ بِعَهْدِهِۦ مِنَ ٱللَّهِ ۚ فَٱسْتَبْشِرُوا۟
بِبَيْعِكُمُ ٱلَّذِى بَايَعْتُم بِهِۦ ۚ وَذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ
﴿١١١﴾

(107) Waɗanda kuwa suka gina masallaci don cutarwa[1] da kafirci da rarraba kawunan muminai da kuma ba da mafaka ga wanda ya yaƙi Allah da Manzonsa tun da can. Kuma lalle za su rantse da Allah cewa ba su yi nufin komai ba sai abu mafi kyau, Allah kuwa Yana ba da shaidar cewa lalle su tabbas maƙaryata ne

(108) Kada ka yi salla a cikinsa har abada. Haƙiƙa masallacin da aka ɗora harsashinsa tun daga ranar farko a kan taƙawa shi ya cancanci ka yi salla a cikinsa. A cikinsa akwai wasu mazaje da suke so su tsarkaka. Allah kuwa Yana son masu tsarkaka

(109) Yanzu wanda ya sanya harsashin gininsa a kan taƙawa ga Allah da (neman) yardarsa[2] shi ya fi ko kuwa wanda ya sanya harshashin gininsa a gefen rami mai zabtarewa, sai ya rubta da shi cikin wutar Jahannama? Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane azzalumai

(110) Ginin nasu da suka yi ba zai daina zama abin kokwanto a zukatansu ba har sai zukatan nasu sun tsittsinke. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima

(111) Lalle Allah Ya sayi rayuka da dukiyoyin muminai daga wurinsu cewa suna da Aljanna: Za su yi yaƙi saboda Allah, sai su kashe su ma kuma a kashe su. Alƙawari ne na gaskiya da Ya ɗaukar wa kansa a cikin Attaura da Linjila da Alƙur'ani. Wane ne ya fi Allah cika alƙawarinsa? Saboda haka sai ku yi farin ciki da cinikin nan naku da kuka yi da Shi. Wannan kuwa shi ne rabo mai girma

(1) Waɗanda suka ware suka gina masallacinsu don cutar da Annabi ( ) da muminai da raba kawunan Musulmi da ba wa maƙiya Musulmi mafaka.

(2) Shi ne masallacin Manzon Allah ( ). Da yawa daga cikin malaman tafsiri suna ganin shi ne masallacin Kuba. Wasu kuma sun ce ana nufin duka biyun.

ٱلتَّـٰٓئِبُونَ ٱلْعَـٰبِدُونَ ٱلْحَـٰمِدُونَ ٱلسَّـٰٓئِحُونَ
ٱلرَّٰكِعُونَ ٱلسَّـٰجِدُونَ ٱلْـَٔامِرُونَ بِٱلْمَعْرُوفِ
وَٱلنَّاهُونَ عَنِ ٱلْمُنكَرِ وَٱلْحَـٰفِظُونَ لِحُدُودِ ٱللَّهِ ۗ
وَبَشِّرِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١١٢﴾ مَا كَانَ لِلنَّبِيِّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟
أَن يَسْتَغْفِرُوا۟ لِلْمُشْرِكِينَ وَلَوْ كَانُوٓا۟ أُو۟لِى قُرْبَىٰ
مِنۢ بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمْ أَنَّهُمْ أَصْحَـٰبُ ٱلْجَحِيمِ ﴿١١٣﴾ وَمَا
كَانَ ٱسْتِغْفَارُ إِبْرَٰهِيمَ لِأَبِيهِ إِلَّا عَن مَّوْعِدَةٍ وَعَدَهَآ
إِيَّاهُ فَلَمَّا تَبَيَّنَ لَهُۥٓ أَنَّهُۥ عَدُوٌّ لِّلَّهِ تَبَرَّأَ مِنْهُ ۚ إِنَّ إِبْرَٰهِيمَ
لَأَوَّٰهٌ حَلِيمٌ ﴿١١٤﴾ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُضِلَّ قَوْمًۢا بَعْدَ إِذْ
هَدَىٰهُمْ حَتَّىٰ يُبَيِّنَ لَهُم مَّا يَتَّقُونَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَىْءٍ
عَلِيمٌ ﴿١١٥﴾ إِنَّ ٱللَّهَ لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ يُحْىِۦ
وَيُمِيتُ ۚ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن وَلِىٍّ وَلَا نَصِيرٍ ﴿١١٦﴾
لَّقَد تَّابَ ٱللَّهُ عَلَى ٱلنَّبِىِّ وَٱلْمُهَـٰجِرِينَ وَٱلْأَنصَارِ ٱلَّذِينَ
ٱتَّبَعُوهُ فِى سَاعَةِ ٱلْعُسْرَةِ مِنۢ بَعْدِ مَا كَادَ يَزِيغُ قُلُوبُ
فَرِيقٍ مِّنْهُمْ ثُمَّ تَابَ عَلَيْهِمْ ۚ إِنَّهُۥ بِهِمْ رَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿١١٧﴾

(112) Masu tuba, masu bauta, masu godiya, masu azumi, masu ruku'i, masu sujjada, masu yin umarni da aikin alheri masu kuma hani ga mummunan aiki, da masu kiyaye iyakokin Allah. To sai ka yi wa muminai (masu irin waɗannan siffofin) albishir

(113) Bai kamata ba ga Annabi da waɗanda suka yi imani su nema wa mushrikai gafara, ko da kuwa sun kasance dangi ne na kusa, bayan kuwa ya riga ya bayyana gare su cewa lalle su 'yan wuta ne

(114) Neman gafarar Ibrahimu kuwa ga babansa bai kasance ba sai don kawai alƙawarin da ya yi masa ne. To lokacin da ya bayyana gare shi cewa shi maƙiyin Allah ne sai ya nesanta kansa da shi. Lalle Ibrahimu ya tabbata mai yawan bautar Allah ne, mai haƙuri

(115) Allah kuwa ba zai taɓa ɓatar da wasu mutane ba bayan Ya riga Ya shiryar da su, har sai Ya bayyana musu abin da za su kiyaye. Lalle Allah Masanin komai ne

(116) Lalle Allah Shi ne Mai mulkin sammai da ƙasa, Yana rayawa kuma Yana kashewa. Ba ku da wani majiɓincin lamarinku in ban da Allah, ba ku kuma da wani mai taimako

(117) Tabbas haƙiƙa Allah Ya yafe wa Annabi da masu hijira da kuma Ansaru waɗanda suka bi shi a lokacin tsanani bayan har zukatan wasu ƙungiyoyi daga cikinsu sun kusa su karkace, sannan (Allah) Ya karɓi tubansu. Lalle Shi Mai tausasawa ne, Mai jin ƙai a gare su

وَعَلَى ٱلثَّلَٰثَةِ ٱلَّذِينَ خُلِّفُواْ حَتَّىٰٓ إِذَا ضَاقَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلۡأَرۡضُ
بِمَا رَحُبَتۡ وَضَاقَتۡ عَلَيۡهِمۡ أَنفُسُهُمۡ وَظَنُّوٓاْ أَن لَّا مَلۡجَأَ
مِنَ ٱللَّهِ إِلَّآ إِلَيۡهِ ثُمَّ تَابَ عَلَيۡهِمۡ لِيَتُوبُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ
ٱلرَّحِيمُ ﴿١١٨﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَكُونُواْ مَعَ
ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿١١٩﴾ مَا كَانَ لِأَهۡلِ ٱلۡمَدِينَةِ وَمَنۡ حَوۡلَهُم
مِّنَ ٱلۡأَعۡرَابِ أَن يَتَخَلَّفُواْ عَن رَّسُولِ ٱللَّهِ وَلَا يَرۡغَبُواْ
بِأَنفُسِهِمۡ عَن نَّفۡسِهِۦۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ لَا يُصِيبُهُمۡ ظَمَأٞ
وَلَا نَصَبٞ وَلَا مَخۡمَصَةٞ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَا يَطَـُٔونَ مَوۡطِئٗا
يَغِيظُ ٱلۡكُفَّارَ وَلَا يَنَالُونَ مِنۡ عَدُوّٖ نَّيۡلًا إِلَّا كُتِبَ
لَهُم بِهِۦ عَمَلٞ صَٰلِحٌۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجۡرَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ
﴿١٢٠﴾ وَلَا يُنفِقُونَ نَفَقَةٗ صَغِيرَةٗ وَلَا كَبِيرَةٗ وَلَا يَقۡطَعُونَ
وَادِيًا إِلَّا كُتِبَ لَهُمۡ لِيَجۡزِيَهُمُ ٱللَّهُ أَحۡسَنَ مَا كَانُواْ
يَعۡمَلُونَ ﴿١٢١﴾ * وَمَا كَانَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ لِيَنفِرُواْ كَآفَّةٗۚ
فَلَوۡلَا نَفَرَ مِن كُلِّ فِرۡقَةٖ مِّنۡهُمۡ طَآئِفَةٞ لِّيَتَفَقَّهُواْ فِي ٱلدِّينِ
وَلِيُنذِرُواْ قَوۡمَهُمۡ إِذَا رَجَعُوٓاْ إِلَيۡهِمۡ لَعَلَّهُمۡ يَحۡذَرُونَ ﴿١٢٢﴾

(118) Kuma (Ya yafe wa) mutanen nan guda uku waɗanda aka dakatar da karɓar tubansu[1], har sai yayin da duniya ta yi musu ƙunci duk da yalwarta, kuma zukatansu suka ƙuntata, suka tabbatar da cewa dai babu wata mafaka daga Allah sai dai a wajensa. Sannan sai Ya yi musu muwafaƙar tuba don su tuba. Lalle Allah Shi ne Mai yawan karɓar tuba, Mai jin ƙai
(119) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Allah kuma ku zama tare da masu gaskiya

(120) Bai kamata ba ga mutanen Madina da waɗanda suke kewaye da su daga mazauna ƙauye su noƙe su ƙi bin Manzon Allah, ko kuma su zaɓi kansu fiye da shi. Wannan kuwa saboda ba wata ƙishirwa ko wahala ko yunwa da za ta same su a kan hanyar Allah, kuma ba za su taka wani wuri ba da zai ɓata wa kafirai rai, kuma ba za su tafka wa abokan gaba wata hasara ba sai an rubuta musu lada saboda shi (wato kowane ɗaya daga abubuwan da aka zana). Lalle Allah ba Ya tozarta ladan masu kyautatawa
(121) Ba kuma za su bayar da wata sadaka ba, ƙarama ko kuma babba, kuma ba wani kwazazzabo da za su keta sai an rubuta musu ladansu don Allah Ya saka musu da mafi kyawun abin da suka zamanto suna aikatawa
(122) Bai kamata muminai su fita yaƙi gaba ɗaya ba. Me zai hana wasu jama'a daga kowace ƙabila (su zauna) don su koyi ilimin addini, su kuma yi wa mutanensu gargaɗi idan sun dawo musu don su kiyaye (dokokin Allah)?

(1) Su ne sahabban nan uku, watau Ka'abu ɗan Maliku da Muraratu ɗan Rabi'atu da Hilal ɗan Umayyatu Al-Waƙifi. Sun ƙi fita yaƙin Tabuka tare da Annabi ( ) ba tare da wani uzuri ba.

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قَٰتِلُواْ ٱلَّذِينَ يَلُونَكُم مِّنَ ٱلۡكُفَّارِ
وَلۡيَجِدُواْ فِيكُمۡ غِلۡظَةٗۚ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلۡمُتَّقِينَ
١٢٣ وَإِذَا مَآ أُنزِلَتۡ سُورَةٞ فَمِنۡهُم مَّن يَقُولُ أَيُّكُمۡ زَادَتۡهُ
هَٰذِهِۦٓ إِيمَٰنٗاۚ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فَزَادَتۡهُمۡ إِيمَٰنٗا وَهُمۡ
يَسۡتَبۡشِرُونَ ١٢٤ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ فَزَادَتۡهُمۡ
رِجۡسًا إِلَىٰ رِجۡسِهِمۡ وَمَاتُواْ وَهُمۡ كَٰفِرُونَ ١٢٥ أَوَلَا
يَرَوۡنَ أَنَّهُمۡ يُفۡتَنُونَ فِي كُلِّ عَامٖ مَّرَّةً أَوۡ مَرَّتَيۡنِ
ثُمَّ لَا يَتُوبُونَ وَلَا هُمۡ يَذَّكَّرُونَ ١٢٦ وَإِذَا مَآ
أُنزِلَتۡ سُورَةٞ نَّظَرَ بَعۡضُهُمۡ إِلَىٰ بَعۡضٍ هَلۡ يَرَىٰكُم
مِّنۡ أَحَدٖ ثُمَّ ٱنصَرَفُواْۚ صَرَفَ ٱللَّهُ قُلُوبَهُم بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ
لَّا يَفۡقَهُونَ ١٢٧ لَقَدۡ جَآءَكُمۡ رَسُولٞ مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ
عَزِيزٌ عَلَيۡهِ مَا عَنِتُّمۡ حَرِيصٌ عَلَيۡكُم بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ
رَءُوفٞ رَّحِيمٞ ١٢٨ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَقُلۡ حَسۡبِيَ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ
إِلَّا هُوَۖ عَلَيۡهِ تَوَكَّلۡتُۖ وَهُوَ رَبُّ ٱلۡعَرۡشِ ٱلۡعَظِيمِ ١٢٩

سُورَةُ يُونُسَ

(123) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yaƙi kafirai waɗanda suke maƙota da ku, kuma su sami kausasawa daga wajenku. Ku kuma sani cewa Allah Yana tare da masu taƙawa
(124) Idan kuwa aka saukar da wata sura, daga cikinsu akwai waɗanda suke cewa: “Wane ne daga cikinku wannan ta ƙara masa imani?” To amma waɗanda suka yi imani su kam ta ƙara musu imani alhali suna cike da farin ciki
(125) Amma kuma waɗanda suke da munafunci a zukatansu sai (surar) ta ƙara musu wata dauɗa a kan dauɗarsu (ta munafunci) suka kuma mutu suna kafirai
(126) Shin yanzu ba sa ganin cewa ana jarrabar su a kowace shekara sau ɗaya ko sau biyu, sannan ba sa tuba kuma ba sa wa’azantuwa?
(127) Idan kuma an saukar da wata surar sai su kalli junansu (su ce): “Shin akwai wani mai ganin ku?” Sannan sai su juya. To Allah Ya juyar da zukatansu saboda su mutane ne da ba sa fahimta
(128) Haƙiƙa Manzo ya zo muku daga jinsinku; abin da zai wahalar da ku yana damun sa; mai kwaɗayin alheri ne gare ku, mai tausayawa kuma mai jin ƙai ga muminai
(129) To idan sun ba da baya sai ka ce: “Allah Ya ishe ni, babu wani abin bautawa da gaskiya sai Shi, a gare Shi kaɗai na dogara; kuma Shi ne Ubangijin Al’arshi mai girma.”

Sura Yunus

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓرٓ ۚ تِلْكَ ءَايَٰتُ ٱلْكِتَٰبِ ٱلْحَكِيمِ ﴿١﴾ أَكَانَ لِلنَّاسِ عَجَبًا
أَنْ أَوْحَيْنَآ إِلَىٰ رَجُلٍ مِّنْهُمْ أَنْ أَنذِرِ ٱلنَّاسَ وَبَشِّرِ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوٓا۟ أَنَّ لَهُمْ قَدَمَ صِدْقٍ عِندَ رَبِّهِمْ ۗ قَالَ ٱلْكَٰفِرُونَ
إِنَّ هَٰذَا لَسَٰحِرٌ مُّبِينٌ ﴿٢﴾ إِنَّ رَبَّكُمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضَ فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ عَلَى ٱلْعَرْشِ ۖ يُدَبِّرُ ٱلْأَمْرَ
مَا مِن شَفِيعٍ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ إِذْنِهِۦ ۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ فَٱعْبُدُوهُ ۚ
أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ﴿٣﴾ إِلَيْهِ مَرْجِعُكُمْ جَمِيعًا ۖ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقًّا ۚ إِنَّهُۥ
يَبْدَؤُا۟ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ لِيَجْزِىَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟
ٱلصَّٰلِحَٰتِ بِٱلْقِسْطِ ۚ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لَهُمْ شَرَابٌ مِّنْ حَمِيمٍ
وَعَذَابٌ أَلِيمٌۢ بِمَا كَانُوا۟ يَكْفُرُونَ ﴿٤﴾ هُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ ٱلشَّمْسَ
ضِيَآءً وَٱلْقَمَرَ نُورًا وَقَدَّرَهُۥ مَنَازِلَ لِتَعْلَمُوا۟ عَدَدَ ٱلسِّنِينَ
وَٱلْحِسَابَ ۚ مَا خَلَقَ ٱللَّهُ ذَٰلِكَ إِلَّا بِٱلْحَقِّ ۚ يُفَصِّلُ ٱلْءَايَٰتِ
لِقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ﴿٥﴾ إِنَّ فِى ٱخْتِلَٰفِ ٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ وَمَا خَلَقَ
ٱللَّهُ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَتَّقُونَ ﴿٦﴾

(1) ALIF LAM RA[1]. Wadannan ayoyin littafi ne (wato Alkur'ani) mai hikima
(2) Shin ya zama abin mamaki ga mutane cewar Mun yi wahayi zuwa ga wani mutum daga cikinsu, cewa: "Ka gargadi mutane, kuma ka yi wa wadanda suka yi imani albishir cewa suna da babban matsayi wurin Ubangijinsu? Sai kafirai suka ce: "Lalle wannan tabbas mai sihiri ne mai bayyana (sihirinsa)."
(3) Lalle Ubangijinku Shi ne Allah wanda Ya halicci sammai da ƙasa cikin kwana shida, sannan Ya daidaita a kan Al'arshi[2]; Yana tsara al'amari (yadda Ya ga dama). Babu wani mai ceto sai da izininsa. Wannan Shi ne Allah Ubangijinku. To sai ku bauta masa. Ashe ba za ku wa'azantu ba?
(4) Zuwa gare Shi ne makomarku take gaba daya; alƙawarin Allah ne da gaske. Lalle Shi ne Yake farar da halitta sannan Ya maido da ita (bayan mutuwa) don Ya saka wa wadanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari da adalci. Wadanda suka kafirce kuwa suna da abin sha mai tsananin ƙuna da kuma azaba mai radadi saboda kafircewa da suke yi
(5) Lalle game da sassaɓawar dare da rana da kuma abubuwan da Allah Ya halitta cikin sammai da ƙasa akwai ayoyi ga mutanen da suke kiyaye dokokin Allah
(6) Lalle game da sassaɓawar dare da rana da kuma abubuwan da Allah Ya halitta cikin sammai da ƙasa akwai ayoyi ga mutanen da suke kiyaye dokokin Allah

(1) Duba Suratul Baƙara aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Duba Suratul A'araf aya ta 54. hashiya ta 126.

إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يَرۡجُونَ لِقَآءَنَا وَرَضُواْ بِٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَٱطۡمَأَنُّواْ
بِهَا وَٱلَّذِينَ هُمۡ عَنۡ ءَايَٰتِنَا غَٰفِلُونَ ٧ أُوْلَٰٓئِكَ مَأۡوَىٰهُمُ
ٱلنَّارُ بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٨ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
ٱلصَّٰلِحَٰتِ يَهۡدِيهِمۡ رَبُّهُم بِإِيمَٰنِهِمۡۖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهِمُ
ٱلۡأَنۡهَٰرُ فِي جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ٩ دَعۡوَىٰهُمۡ فِيهَا سُبۡحَٰنَكَ
ٱللَّهُمَّ وَتَحِيَّتُهُمۡ فِيهَا سَلَٰمٞۚ وَءَاخِرُ دَعۡوَىٰهُمۡ أَنِ ٱلۡحَمۡدُ
لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٠ * وَلَوۡ يُعَجِّلُ ٱللَّهُ لِلنَّاسِ ٱلشَّرَّ
ٱسۡتِعۡجَالَهُم بِٱلۡخَيۡرِ لَقُضِيَ إِلَيۡهِمۡ أَجَلُهُمۡۖ فَنَذَرُ ٱلَّذِينَ
لَا يَرۡجُونَ لِقَآءَنَا فِي طُغۡيَٰنِهِمۡ يَعۡمَهُونَ ١١ وَإِذَا مَسَّ ٱلۡإِنسَٰنَ
ٱلضُّرُّ دَعَانَا لِجَنۡۢبِهِۦٓ أَوۡ قَاعِدًا أَوۡ قَآئِمٗا فَلَمَّا كَشَفۡنَا
عَنۡهُ ضُرَّهُۥ مَرَّ كَأَن لَّمۡ يَدۡعُنَآ إِلَىٰ ضُرّٖ مَّسَّهُۥۚ كَذَٰلِكَ زُيِّنَ
لِلۡمُسۡرِفِينَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٢ وَلَقَدۡ أَهۡلَكۡنَا ٱلۡقُرُونَ
مِن قَبۡلِكُمۡ لَمَّا ظَلَمُواْ وَجَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ وَمَا كَانُواْ
لِيُؤۡمِنُواْۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ١٣ ثُمَّ جَعَلۡنَٰكُمۡ
خَلَٰٓئِفَ فِي ٱلۡأَرۡضِ مِنۢ بَعۡدِهِمۡ لِنَنظُرَ كَيۡفَ تَعۡمَلُونَ ١٤

(7) Lalle waɗanda ba sa tsammanin gamuwa da Mu, suka kuma yarda da rayuwar duniya, kuma suka nutsu da ita, da kuma waɗanda suke gafala daga ayoyinmu
(8) Waɗanan makomarsu wuta ce saboda abin da suka kasance suna aikatawa
(9) Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, Ubangijinsu zai shirye su saboda imaninsu: ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu cikin aljannatai na ni'ima
(10) Addu'arsu a cikinta: "Muna tsarkake Ka ya Allah", gaisuwarsu kuma a cikinta "Salamun" (watau aminci).

Karshen addu'arsu kuma ita ce: "Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai."
(11) Da dai Allah zai gaggauta (karɓar addu'ar) mutane ta sharri kamar yadda yake gaggauta ta alheri to da ƙarshen rayuwarsu ya zo. Sai dai Mukan bar waɗanda ba sa tsammanin haɗuwa da Mu cikin shisshiginsu su yi ta ɗimuwa
(12) Idan kuma wata cuta ta sami mutum, sai ya roƙe Mu, a kishingiɗe ne ko a zaune ko kuwa a tsaye. To lokacin da Muka yaye masa cutarsa sai ya ci gaba (da halinsa) kamar bai taɓa roƙon Mu game da wata cuta da ta shafe shi ba. Kamar haka ne aka ƙawata wa maɓarnata abin da suka kasance suna aikatawa
(13) Haƙiƙa kuma Mun hallaka al'ummun da suka gabace ku, lokacin da suka yi zalunci, kuma manzanninsu suka zo musu da (hujjoji) mabayyana, sai ba su zamana sun yi imani ba. Kamar haka ne Muke saka wa mutane masu laifi
(14) Sannan bayansu Muka mayar da ku madadinsu a bayan ƙasa don Mu ga me za ku aikata

وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَاتُنَا بَيِّنَٰتٍ قَالَ ٱلَّذِينَ لَا يَرْجُونَ
لِقَآءَنَا ٱئْتِ بِقُرْءَانٍ غَيْرِ هَٰذَآ أَوْ بَدِّلْهُ ۚ قُلْ مَا يَكُونُ
لِىٓ أَنْ أُبَدِّلَهُۥ مِن تِلْقَآئِ نَفْسِىٓ ۖ إِنْ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ إِلَىَّ ۖ
إِنِّىٓ أَخَافُ إِنْ عَصَيْتُ رَبِّى عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿١٥﴾ قُل
لَّوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا تَلَوْتُهُۥ عَلَيْكُمْ وَلَآ أَدْرَىٰكُم بِهِۦ ۖ
فَقَدْ لَبِثْتُ فِيكُمْ عُمُرًا مِّن قَبْلِهِۦٓ ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿١٦﴾
فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوْ كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِهِۦٓ ۚ
إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿١٧﴾ وَيَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
مَا لَا يَضُرُّهُمْ وَلَا يَنفَعُهُمْ وَيَقُولُونَ هَٰٓؤُلَآءِ شُفَعَٰٓؤُنَا
عِندَ ٱللَّهِ ۚ قُلْ أَتُنَبِّـُٔونَ ٱللَّهَ بِمَا لَا يَعْلَمُ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا
فِى ٱلْأَرْضِ ۚ سُبْحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿١٨﴾ وَمَا
كَانَ ٱلنَّاسُ إِلَّآ أُمَّةً وَٰحِدَةً فَٱخْتَلَفُوا۟ ۚ وَلَوْلَا كَلِمَةٌ
سَبَقَتْ مِن رَّبِّكَ لَقُضِىَ بَيْنَهُمْ فِيمَا فِيهِ يَخْتَلِفُونَ
﴿١٩﴾ وَيَقُولُونَ لَوْلَآ أُنزِلَ عَلَيْهِ ءَايَةٌ مِّن رَّبِّهِۦ ۖ فَقُلْ إِنَّمَا
ٱلْغَيْبُ لِلَّهِ فَٱنتَظِرُوٓا۟ إِنِّى مَعَكُم مِّنَ ٱلْمُنتَظِرِينَ ﴿٢٠﴾

(15) Idan kuma ana karanta musu ayoyinmu bayyanannu sai waɗanda ba sa tsammanin haɗuwa da mu su ce: “Ka zo da wani alƙur’anin ba wannan ba, ko kuma ka canja shi.” Ka ce (da su): “Bai dace da ni ba in canja shi da raɗin kaina. Ni ba abin da nake bi sai abin da kawai aka yo mini wahayi. Lalle ni dai ina tsoron azabar rana mai girma idan na saba wa Ubangijina.”

(16) Ka ce: “Da Allah Ya ga dama da ban karanta muku shi ba, kuma da (Allah) bai sanar da ku shi ba, domin haƙiƙa na zauna cikinku shekaru masu yawa[1] tun gabaninsa. Me ya sa ba za ku hankalta ba?”

(17) To ba wanda ya fi zalunci irin wanda ya ƙirƙira wa Allah ƙarya ko kuma ya ƙaryata ayoyinsa. Lalle masu babban laifi ba za su rabauta ba

(18) Suna kuma bauta wa wani ba Allah ba, abin da ba zai cutar da su ba ba kuma zai amfane su ba, suna kuma cewa: “Waɗannan su ne masu ceton mu a wurin Allah.” Ka ce: “Shin yanzu za ku ba Allah labarin abin da bai sani ba ne a cikin sammai ko kuma a bayan ƙasa? Tsarki ya tabbata a gare Shi Ya kuma ɗaukaka daga abin da suke shirka da Shi.”

(19) A da can mutane sun zamanto al’umma ɗaya ce (a kan tauhidi), to sai suka sassaba. Da ba don wata kalma da ta gabata daga Ubangijinka[2] ba, to da an yi hukunci a tsakaninsu game da abin da suke sassaɓawa a kai

(20) Suna kuma cewa: “Don me ba a saukar masa da wata aya daga Ubangijinsa ba?” To ka ce: “Sanin gaibu na Allah ne kawai, sai ku saurara, lalle ni ma ina tare da ku cikin masu sauraro.”

(1) Annabi ( ) ya zauna a cikin mutanensa shekara arba’in kafin a fara yi masa wahayi.

(2) Watau hukuncinsa na cewa zai saurara wa mushirikai har zuwa ranar alƙiyama.

وَإِذَآ أَذَقْنَا ٱلنَّاسَ رَحْمَةً مِّنۢ بَعْدِ ضَرَّآءَ مَسَّتْهُمْ إِذَا لَهُم مَّكْرٌ
فِىٓ ءَايَاتِنَا ۚ قُلِ ٱللَّهُ أَسْرَعُ مَكْرًا ۚ إِنَّ رُسُلَنَا يَكْتُبُونَ مَا تَمْكُرُونَ
﴿٢١﴾ هُوَ ٱلَّذِى يُسَيِّرُكُمْ فِى ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا كُنتُمْ فِى ٱلْفُلْكِ
وَجَرَيْنَ بِهِم بِرِيحٍ طَيِّبَةٍ وَفَرِحُوا۟ بِهَا جَآءَتْهَا رِيحٌ عَاصِفٌ
وَجَآءَهُمُ ٱلْمَوْجُ مِن كُلِّ مَكَانٍ وَظَنُّوٓا۟ أَنَّهُمْ أُحِيطَ بِهِمْ
دَعَوُا۟ ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ لَئِنْ أَنجَيْتَنَا مِنْ هَٰذِهِۦ لَنَكُونَنَّ
مِنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿٢٢﴾ فَلَمَّآ أَنجَىٰهُمْ إِذَا هُمْ يَبْغُونَ فِى ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ
ٱلْحَقِّ ۗ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّمَا بَغْيُكُمْ عَلَىٰٓ أَنفُسِكُم ۖ مَّتَٰعَ ٱلْحَيَوٰةِ
ٱلدُّنْيَا ۖ ثُمَّ إِلَيْنَا مَرْجِعُكُمْ فَنُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٢٣﴾
إِنَّمَا مَثَلُ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا كَمَآءٍ أَنزَلْنَٰهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَٱخْتَلَطَ
بِهِۦ نَبَاتُ ٱلْأَرْضِ مِمَّا يَأْكُلُ ٱلنَّاسُ وَٱلْأَنْعَٰمُ حَتَّىٰٓ إِذَآ
أَخَذَتِ ٱلْأَرْضُ زُخْرُفَهَا وَٱزَّيَّنَتْ وَظَنَّ أَهْلُهَآ أَنَّهُمْ قَٰدِرُونَ
عَلَيْهَآ أَتَىٰهَآ أَمْرُنَا لَيْلًا أَوْ نَهَارًا فَجَعَلْنَٰهَا حَصِيدًا كَأَن لَّمْ تَغْنَ
بِٱلْأَمْسِ ۚ كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ﴿٢٤﴾ وَٱللَّهُ يَدْعُوٓا۟
إِلَىٰ دَارِ ٱلسَّلَٰمِ وَيَهْدِى مَن يَشَآءُ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٢٥﴾

(21) Idan kuma Muka ɗanɗana wa mutane dadi bayan wahala ta same su, sai ga su suna ƙulla makirci ga ayoyinmu. Ka ce: “Allah Ya fi gaggawar (sakayya a kan) makirci.” Lalle manzanninmu suna rubuta abin da kuke ƙullawa na makirci

(22) Shi ne Wanda Yake tafiyar da ku a tudu da cikin ruwa, har lokacin da kuka shiga cikin jiragen ruwa, (jiragen) kuwa suka yi gudu da su tare da iska mai daɗi, suka kuma yi farin ciki da su (jiragen) sai kuma wata iska mai ƙarfi ta zo musu; raƙumin ruwa kuma ya zo musu ta kowane wuri, suka kuma tabbatar cewa dai su kam an rutsa da su, sai kuma suka roƙi Allah suna masu tsarkake addini gare Shi (suna cewa): “Tabbas idan Ka tserar da mu daga wannan, lalle haƙiƙa za mu zamo cikin masu godiya.”

(23) To lokacin da Ya tserar da su sai ga su suna ɓarna a bayan ƙasa ba da gaskiya ba. Ya ku mutane, haƙiƙa (sakamakon) ɓarnarku a kanku kawai yake; ku ɗan ji daɗin rayuwar duniya; sannan (daga ƙarshe) zuwa gare Mu ne makomarku take, sannan mu ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa

(24) Misalin rayuwar duniya kawai kamar ruwa ne da Muka saukar da shi daga sama, to sai shukokin da suke kan ƙasa suka cuɗanya da shi daga abin da mutane da dabbobi suke ci; har lokacin da ƙasa ta ƙawata (da shi) ta kuma yi ado; masu ita kuma suka sakankance cewa su masu ikon cin amfaninta ne, sai ƙaddararmu ta zo mata cikin dare ko rana, sai Muka mayar da ita girbabbiya kamar daɗai ba ta rayu ba a jiya. Kamar haka Muke bayyana ayoyi ga mutanen da suke tunani

(25) Allah kuwa Yana kira ne zuwa gidan aminci (wato Aljanna), Yana kuma shiryar da wanda Ya ga dama zuwa tafarki madaidaici


* لِّلَّذِينَ أَحْسَنُوا۟ ٱلْحُسْنَىٰ وَزِيَادَةٌ ۖ وَلَا يَرْهَقُ وُجُوهَهُمْ قَتَرٌ
وَلَا ذِلَّةٌ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ ۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿٢٦﴾ وَٱلَّذِينَ
كَسَبُوا۟ ٱلسَّيِّـَٔاتِ جَزَآءُ سَيِّئَةٍ بِمِثْلِهَا وَتَرْهَقُهُمْ ذِلَّةٌ ۖ مَّا لَهُم
مِّنَ ٱللَّهِ مِنْ عَاصِمٍ ۖ كَأَنَّمَآ أُغْشِيَتْ وُجُوهُهُمْ قِطَعًا مِّنَ ٱلَّيْلِ
مُظْلِمًا ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ ۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿٢٧﴾ وَيَوْمَ نَحْشُرُهُمْ
جَمِيعًا ثُمَّ نَقُولُ لِلَّذِينَ أَشْرَكُوا۟ مَكَانَكُمْ أَنتُمْ وَشُرَكَآؤُكُمْ ۚ فَزَيَّلْنَا
بَيْنَهُمْ ۖ وَقَالَ شُرَكَآؤُهُم مَّا كُنتُمْ إِيَّانَا تَعْبُدُونَ ﴿٢٨﴾ فَكَفَىٰ بِٱللَّهِ
شَهِيدًۢا بَيْنَنَا وَبَيْنَكُمْ إِن كُنَّا عَنْ عِبَادَتِكُمْ لَغَٰفِلِينَ ﴿٢٩﴾
هُنَالِكَ تَبْلُوا۟ كُلُّ نَفْسٍ مَّآ أَسْلَفَتْ ۚ وَرُدُّوٓا۟ إِلَى ٱللَّهِ مَوْلَىٰهُمُ
ٱلْحَقِّ ۖ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ﴿٣٠﴾ قُلْ مَن يَرْزُقُكُم مِّنَ
ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ أَمَّن يَمْلِكُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ وَمَن يُخْرِجُ
ٱلْحَىَّ مِنَ ٱلْمَيِّتِ وَيُخْرِجُ ٱلْمَيِّتَ مِنَ ٱلْحَىِّ وَمَن يُدَبِّرُ ٱلْأَمْرَ ۚ
فَسَيَقُولُونَ ٱللَّهُ ۚ فَقُلْ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿٣١﴾ فَذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمُ
ٱلْحَقُّ ۖ فَمَاذَا بَعْدَ ٱلْحَقِّ إِلَّا ٱلضَّلَٰلُ ۖ فَأَنَّىٰ تُصْرَفُونَ ﴿٣٢﴾ كَذَٰلِكَ
حَقَّتْ كَلِمَتُ رَبِّكَ عَلَى ٱلَّذِينَ فَسَقُوٓا۟ أَنَّهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿٣٣﴾

(26) Waɗanda suka kyautata aiki suna da sakamako mafi kyau (watau Aljanna) da kuma ƙari[1]. Wani ƙunci da ƙasƙanci kuma ba za su same su ba. Waɗannan su ne ‘yan Aljanna; su masu dawwama ne a cikinta
(27) Waɗanda kuma suka yi mummunan aiki, to sakamakon mummunan aiki irinsa ne, kuma ƙasƙanci zai lulluɓe su; ba su da wani mai kare su daga (azabar) Allah; kamar dai an lulluɓe fuskokinsu ne da wani yanki na dare mai duhu ƙirin. Waɗannan su ne ‘yan wuta; su kuma masu dawwama ne a cikinta
(28) (Ka tuna) ranar da za mu tara su ga baki ɗaya, sannan mu ce da waɗanda suka yi shirka: “Ku tsaya cak a wurarenku ku da abokan tarayyarku”. Sai kuma mu raba tsakaninsu; sai abokan tarayyarsu kuma su ce: “Ba mu ne kuka kasance kuna bauta wa ba
(29) “To kuma Allah Ya isa shaida tsakaninmu da ku: mu kam lalle mun kasance ba mu ma san kuna bautar mu ba.”
(30) A can ne kowane rai zai samu sakamakon abin da ya gabatar (a duniya). An kuma mayar da su zuwa ga Allah Majiɓincinsu na gaskiya; abin da kuma suka kasance suna ƙirƙira ya ɓace musu
(31) Ka ce: “Wane ne yake arzuta ku ta sama da ƙasa? Ko kuma wane ne mamallakin ji da gani? Kuma wane ne yake fitar da mai rai daga matacce, ya kuma fitar da matacce daga mai rai? Wane ne kuma yake tsara al’amura?” To ai za su ce: “Allah ne.” To ka ce: “Yanzu ba za ku kiyaye dokokinsa ba?”
(32) To wannan Shi ne Allah Ubangijinku na gaskiya. Bayan gaskiya kuwa babu wani abu sai ɓata. To yaya ake karkatar da ku?
(33) Kamar haka ne kalmar Ubangijinka ta tabbata a kan waɗanda suka yi fasiƙanci cewa su ba za su yi imani ba

(1) Watau shi ne ganin Fuskar Allah ( ) bayan shigarsu Aljanna. Duba Muslim #181.

قُلْ هَلْ مِن شُرَكَآئِكُم مَّن يَبْدَؤُا۟ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ ۚ قُلِ ٱللَّهُ يَبْدَؤُا۟
ٱلْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ ۖ فَأَنَّىٰ تُؤْفَكُونَ ﴿٣٤﴾ قُلْ هَلْ مِن شُرَكَآئِكُم مَّن يَهْدِىٓ
إِلَى ٱلْحَقِّ ۚ قُلِ ٱللَّهُ يَهْدِى لِلْحَقِّ ۗ أَفَمَن يَهْدِىٓ إِلَى ٱلْحَقِّ أَحَقُّ أَن
يُتَّبَعَ أَمَّن لَّا يَهِدِّىٓ إِلَّآ أَن يُهْدَىٰ ۖ فَمَا لَكُمْ كَيْفَ تَحْكُمُونَ ﴿٣٥﴾
وَمَا يَتَّبِعُ أَكْثَرُهُمْ إِلَّا ظَنًّا ۚ إِنَّ ٱلظَّنَّ لَا يُغْنِى مِنَ ٱلْحَقِّ شَيْـًٔا ۚ
إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِمَا يَفْعَلُونَ ﴿٣٦﴾ وَمَا كَانَ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانُ أَن يُفْتَرَىٰ
مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَٰكِن تَصْدِيقَ ٱلَّذِى بَيْنَ يَدَيْهِ وَتَفْصِيلَ ٱلْكِتَٰبِ
لَا رَيْبَ فِيهِ مِن رَّبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٣٧﴾ أَمْ يَقُولُونَ ٱفْتَرَىٰهُ ۖ قُلْ فَأْتُوا۟
بِسُورَةٍ مِّثْلِهِۦ وَٱدْعُوا۟ مَنِ ٱسْتَطَعْتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ
﴿٣٨﴾ بَلْ كَذَّبُوا۟ بِمَا لَمْ يُحِيطُوا۟ بِعِلْمِهِۦ وَلَمَّا يَأْتِهِمْ تَأْوِيلُهُۥ ۚ كَذَٰلِكَ
كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ ۖ فَٱنظُرْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٣٩﴾
وَمِنْهُم مَّن يُؤْمِنُ بِهِۦ وَمِنْهُم مَّن لَّا يُؤْمِنُ بِهِۦ ۚ وَرَبُّكَ أَعْلَمُ
بِٱلْمُفْسِدِينَ ﴿٤٠﴾ وَإِن كَذَّبُوكَ فَقُل لِّى عَمَلِى وَلَكُمْ عَمَلُكُمْ ۖ أَنتُم
بَرِيٓـُٔونَ مِمَّآ أَعْمَلُ وَأَنَا۠ بَرِىٓءٌ مِّمَّا تَعْمَلُونَ ﴿٤١﴾ وَمِنْهُم مَّن
يَسْتَمِعُونَ إِلَيْكَ ۚ أَفَأَنتَ تُسْمِعُ ٱلصُّمَّ وَلَوْ كَانُوا۟ لَا يَعْقِلُونَ ﴿٤٢﴾

(34) Ka ce: “Shin daga cikin abokan tarayyarku ko akwai wanda yake ƙaga halitta, sannan ya maimaita ta?” Ka ce: “Allah Shi ne Wanda Yake ƙaga halitta sannan Ya maimaita ta. To ta yaya ake kautar da ku?”

(35) Ka ce: “Shin daga abokan tarayyarku ko akwai wanda yake shiryarwa zuwa gaskiya?” Ka ce: “Allah Shi ne Yake shiryarwa zuwa ga gaskiya. To yanzu wanda yake shiryarwa zuwa gaskiya shi ya fi cancanta a bi, ko kuwa wanda ba ya shiryarwa sai dai a shiryar da shi? To me ya same ku ne? Yaya kuke wannan hukuncin?

(36) Yawancinsu kuma ba abin da suke bi sai zato. Lalle zato ba ya wadatar da komai game da gaskiya. Lalle Allah Masanin abin da suke aikatawa ne

(37) Wannan Alƙur’ani bai yiwuwa a ƙage shi daga (tunanin) wani wanda ba Allah ba, sai dai (shi) gaskatawa ne ga abin da ya gabace shi (na littattafan da aka saukar), kuma bayani ne dalla-dalla na hukunce-hukuncen (da Allah ya saukar); babu kokwanto a cikinsa cewa daga Ubangijin talikai yake

(38) Ko kuma cewa suke yi: “Kagar sa ya yi ne?” Ka ce: “To ku kawo sura (ɗaya tal) irinsa, kuma ku kirawo wanda duk za ku iya (ya taimaka muku) wanda ba Allah ba idan kun kasance masu gaskiya!”

(39) A’a, ba haka ba ne, sun dai ƙaryata abin da ba su da iliminsa ne, kuma har yanzu haƙiƙanin fassararsa ba ta zo musu ba. Kamar haka ne waɗanda suka gabace su suka ƙaryata. To duba ka ga yadda ƙarshen azzalumai ya zama

(40) Daga cikinsu kuma akwai wanda yake yin imani da shi (Alƙur’ani), akwai kuma wanda ba ya yin imani da shi. Ubangijinka kuma Shi ne Mafi sanin maɓarnata

(41) Idan kuwa suka ƙaryata ka, to ka ce: “Aikina nawa ne ku ma aikinku naku ne. Ku babu ruwanku da abin da nake aikatawa, ni ma kuma babu ruwana da abin da kuke aikatawa.”

(42) Daga cikinsu akwai waɗanda suke sauraron ka. Yanzu kai za ka iya jiyar da kurame ko da ba su da hankali?

وَمِنْهُم مَّن يَنظُرُ إِلَيْكَ ۚ أَفَأَنتَ تَهْدِى ٱلْعُمْىَ وَلَوْ كَانُوا۟ لَا يُبْصِرُونَ
﴿٤٣﴾ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَظْلِمُ ٱلنَّاسَ شَيْـًٔا وَلَٰكِنَّ ٱلنَّاسَ أَنفُسَهُمْ
يَظْلِمُونَ ﴿٤٤﴾ وَيَوْمَ يَحْشُرُهُمْ كَأَن لَّمْ يَلْبَثُوٓا۟ إِلَّا سَاعَةً مِّنَ ٱلنَّهَارِ
يَتَعَارَفُونَ بَيْنَهُمْ ۚ قَدْ خَسِرَ ٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِلِقَآءِ ٱللَّهِ وَمَا كَانُوا۟
مُهْتَدِينَ ﴿٤٥﴾ وَإِمَّا نُرِيَنَّكَ بَعْضَ ٱلَّذِى نَعِدُهُمْ أَوْ نَتَوَفَّيَنَّكَ
فَإِلَيْنَا مَرْجِعُهُمْ ثُمَّ ٱللَّهُ شَهِيدٌ عَلَىٰ مَا يَفْعَلُونَ ﴿٤٦﴾ وَلِكُلِّ
أُمَّةٍ رَّسُولٌ ۖ فَإِذَا جَآءَ رَسُولُهُمْ قُضِىَ بَيْنَهُم بِٱلْقِسْطِ وَهُمْ
لَا يُظْلَمُونَ ﴿٤٧﴾ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلْوَعْدُ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ
﴿٤٨﴾ قُل لَّآ أَمْلِكُ لِنَفْسِى ضَرًّا وَلَا نَفْعًا إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُ ۗ لِكُلِّ أُمَّةٍ
أَجَلٌ ۚ إِذَا جَآءَ أَجَلُهُمْ فَلَا يَسْتَـْٔخِرُونَ سَاعَةً وَلَا يَسْتَقْدِمُونَ ﴿٤٩﴾
قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِنْ أَتَىٰكُمْ عَذَابُهُۥ بَيَٰتًا أَوْ نَهَارًا مَّاذَا يَسْتَعْجِلُ مِنْهُ
ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿٥٠﴾ أَثُمَّ إِذَا مَا وَقَعَ ءَامَنتُم بِهِۦٓ ءَآلْـَٰٔنَ وَقَدْ كُنتُم بِهِۦ
تَسْتَعْجِلُونَ ﴿٥١﴾ ثُمَّ قِيلَ لِلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ ذُوقُوا۟ عَذَابَ ٱلْخُلْدِ
هَلْ تُجْزَوْنَ إِلَّا بِمَا كُنتُمْ تَكْسِبُونَ ﴿٥٢﴾ ۞ وَيَسْتَنۢبِـُٔونَكَ
أَحَقٌّ هُوَ ۖ قُلْ إِى وَرَبِّىٓ إِنَّهُۥ لَحَقٌّ ۖ وَمَآ أَنتُم بِمُعْجِزِينَ ﴿٥٣﴾

(43) Daga cikinsu kuma akwai wanda yake kura maka ido. Yanzu kai za ka iya shiryar da makafi ko da ba sa gani?

(44) Lalle Allah ba Ya zaluntar mutane da komai, sai dai mutane kawunansu kawai suke zalunta

(45) Ranar da zai tattara su kuwa (za su ga) kamar ba su zauna ba sai wani ɗan lokaci na rana da suke gane junansu (a cikinsa). Haƙiƙa waɗanda suka ƙaryata gamuwa da Allah sun taɓe, ba su kuma zamanto shiryayyu ba

(46) Ko dai Mu nuna maka sashin abin da Muke musu alkawarinsa ko kuma Mu karɓi ranka, to makomarsu dai gare Mu take, sannan Allah Yana sane da abin da suke aikatawa

(47) Kowacce al'umma kuma tana da manzo. To idan manzonsu ya zo (suka ƙaryata shi) to sai a yi hukunci a tsakaninsu da adalci, su kuma ba za a zalunce su ba

(48) Suna kuma cewa: "To yaushe ne wannan alƙawari (zai zo) idan kun kasance masu gaskiya?"

(49) Ka ce: "Ba na mallakar wata cuta, ko wani amfani ga kaina sai dai abin da Allah Ya ga dama. Kowacce al'umma tana da lokacin (da aka iyakance mata). Idan lokacin nasu ya yi, to ba za su yi jinkiri na sa'a guda ba, kuma ba za su gaggauto ba."

(50) Ka ce: "Yanzu ku ba ni labari (yadda za ku yi) idan azabar Allah ta zo muku da daddare ko da rana; mene ne masu laifi suke yi wa gaggawar zuwansa?

(51) "Shin sai idan (azabar) ta afka (muku) ne za ku yi imani da Shi (Allah)? Sai yanzu ne, alhali kuwa da can kun kasance kuna neman gaggautowarta?"

(52) Sannan aka ce da waɗanda suka yi zalunci: "Ku ɗanɗani azaba mai dawwama; shin za a saka muku (da wani abu ne) in ban da abin da kuka kasance kuna aikatawa?."

(53) Suna kuma tambayar ka cewa: "Yanzu (batun azabar nan) gaskiya ne kuwa?" Ka ce: "I mana, na ko ranste da Allah lalle shi gaskiya ne; ba kuma za ku kuɓuce ba."

وَلَوْ أَنَّ لِكُلِّ نَفْسٍ ظَلَمَتْ مَا فِي ٱلْأَرْضِ لَٱفْتَدَتْ بِهِۦ ۗ وَأَسَرُّوا۟
ٱلنَّدَامَةَ لَمَّا رَأَوُا۟ ٱلْعَذَابَ ۖ وَقُضِىَ بَيْنَهُم بِٱلْقِسْطِ وَهُمْ
لَا يُظْلَمُونَ ﴿٥٤﴾ أَلَآ إِنَّ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۗ أَلَآ إِنَّ
وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٥٥﴾ هُوَ يُحْىِۦ وَيُمِيتُ
وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٥٦﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدْ جَآءَتْكُم مَّوْعِظَةٌ
مِّن رَّبِّكُمْ وَشِفَآءٌ لِّمَا فِي ٱلصُّدُورِ وَهُدًى وَرَحْمَةٌ لِّلْمُؤْمِنِينَ
﴿٥٧﴾ قُلْ بِفَضْلِ ٱللَّهِ وَبِرَحْمَتِهِۦ فَبِذَٰلِكَ فَلْيَفْرَحُوا۟ هُوَ خَيْرٌ مِّمَّا
يَجْمَعُونَ ﴿٥٨﴾ قُلْ أَرَءَيْتُم مَّآ أَنزَلَ ٱللَّهُ لَكُم مِّن رِّزْقٍ
فَجَعَلْتُم مِّنْهُ حَرَامًا وَحَلَٰلًا قُلْ ءَآللَّهُ أَذِنَ لَكُمْ ۖ أَمْ عَلَى
ٱللَّهِ تَفْتَرُونَ ﴿٥٩﴾ وَمَا ظَنُّ ٱلَّذِينَ يَفْتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ
يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ
لَا يَشْكُرُونَ ﴿٦٠﴾ وَمَا تَكُونُ فِى شَأْنٍ وَمَا تَتْلُوا۟ مِنْهُ مِن قُرْءَانٍ
وَلَا تَعْمَلُونَ مِنْ عَمَلٍ إِلَّا كُنَّا عَلَيْكُمْ شُهُودًا إِذْ تُفِيضُونَ
فِيهِ ۚ وَمَا يَعْزُبُ عَن رَّبِّكَ مِن مِّثْقَالِ ذَرَّةٍ فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا فِى
ٱلسَّمَآءِ وَلَآ أَصْغَرَ مِن ذَٰلِكَ وَلَآ أَكْبَرَ إِلَّا فِى كِتَٰبٍ مُّبِينٍ
﴿٦١﴾

(54) Da a ce kowane rai da ya yi zalunci ya mallaki duk abin da yake bayan ƙasa, to lalle da ya fanshi kansa da shi. Suka kuwa ɓoye nadama a lokacin da suka ga azaba; an kuma yi hukunci tsakaninsu na adalci; ba kuma za a zalunce su ba

(55) A saurara, lalle duk abin da yake sammai da ƙasa na Allah ne. A saurara, lalle alƙwarin Allah gaskiya ne, sai dai kuma yawancin mutane ba su sani ba

(56) Shi ne Yake rayawa Yake kuma kashewa, kuma wurinsa za a mai da ku

(57) Ya ku mutane, haƙiƙa gargaɗi ya zo muku daga Ubangijinku da kuma waraka ga abin da yake cikin zukatanku, kuma shiriya ne da rahama ga muminai

(58) Ka ce: "Da falalar Allah da rahamarsa, sai su yi farin ciki da wannan; shi ya fi alheri daga abin da suke tarawa (na dukiya)."


(59) Ka ce (da su): "Ku ba ni labarin abin da Allah Ya saukar muku na arziki, sannan kuka mayar da wani haram wani kuma halal". Ka ce: "Yanzu Allah ne Ya yi muku izinin (yin haka), ko kuwa Allah kuke yi wa ƙage ne?"

(60) Mene ne kuma tsammanin waɗanda suke yi wa Allah ƙagen ƙarya a ranar alƙiyama? Lalle Allah Ma'abocin falala ne ga mutane, sai dai kuma yawancinsu ba sa godewa

(61) Kuma babu wani al'amari da (kai Annabi) kake zamantowa cikinsa, babu kuma wani abu na Alƙur'ani da kake karantawa, kuma babu wani abu da kuke aikatawa (kai da al'ummarka), sai Mun zamanto Muna kallon ku lokacin da kuke kutsawa cikinsa. Kuma babu wani abu da yake ɓoye wa Ubangijinka daidai da ƙwayar komayya, a ƙasa ko a sama ko kuma mafi ƙanƙanta ko mafi girma daga wancan (abin) sai fa yana cikin litttafi mabayyani (Lauhul-Mahafuzu)

أَلَآ إِنَّ أَوْلِيَآءَ ٱللَّهِ لَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٦٢﴾
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَكَانُوا۟ يَتَّقُونَ ﴿٦٣﴾ لَهُمُ ٱلْبُشْرَىٰ
فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَفِى ٱلْـَٔاخِرَةِ ۚ لَا تَبْدِيلَ لِكَلِمَٰتِ
ٱللَّهِ ۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿٦٤﴾ وَلَا يَحْزُنكَ قَوْلُهُمْ ۘ إِنَّ
ٱلْعِزَّةَ لِلَّهِ جَمِيعًا ۚ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٦٥﴾ أَلَآ إِنَّ لِلَّهِ
مَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِى ٱلْأَرْضِ ۗ وَمَا يَتَّبِعُ ٱلَّذِينَ
يَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ شُرَكَآءَ ۚ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ
وَإِنْ هُمْ إِلَّا يَخْرُصُونَ ﴿٦٦﴾ هُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ
ٱلَّيْلَ لِتَسْكُنُوا۟ فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبْصِرًا ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ
لَـَٔايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَسْمَعُونَ ﴿٦٧﴾ قَالُوا۟ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدًا ۗ
سُبْحَٰنَهُۥ ۖ هُوَ ٱلْغَنِىُّ ۖ لَهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۚ
إِنْ عِندَكُم مِّن سُلْطَٰنٍۭ بِهَٰذَا ۚ أَتَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ
مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿٦٨﴾ قُلْ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَفْتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ
لَا يُفْلِحُونَ ﴿٦٩﴾ مَتَٰعٌ فِى ٱلدُّنْيَا ثُمَّ إِلَيْنَا مَرْجِعُهُمْ ثُمَّ
نُذِيقُهُمُ ٱلْعَذَابَ ٱلشَّدِيدَ بِمَا كَانُوا۟ يَكْفُرُونَ ﴿٧٠﴾

(62) A saurara, lalle waliyyan Allah babu wani tsoro a gare su, kuma ba za su yi wani baƙin ciki ba
(63) (Su ne) waɗanda suka yi imani kuma suka kasance masu kiyaye dokokin Allah
(64) Suna da albishir a rayuwar duniya da kuma ta lahira. Babu wani sauyi ga kalmomin Allah. Wannan shi ne babban rabo
(65) Kada kuma wata maganarsu ta baƙanta maka rai. Lalle girma gaba ɗayansa na Allah ne. Shi Mai ji ne, Masani
(66) Ku saurara, lalle duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa na Allah ne. Waɗanda suke bauta wa wani ba Allah ba, ba ababen tarayya (na gaskiya) suke bi ba. Ba abin da suke bi sai mummunan zato, kuma ba abin da suke yi sai shaci-faɗi
(67) Shi ne Wanda Ya sanya muku dare don ku samu nutsuwa, rana kuma don haskakawa. Lalle a game da wannan ba tabbas akwai ayoyi ga mutane masu ji
(68) Suke ce Allah Yana da ɗa! Tsarki ya tabbata gare Shi. Shi Mawadaci ne. Abin da yake cikin sammai da abin da yake ƙasa nasa ne. Ko kuna da wata hujja ne game da wannan? Yanzu kwa riƙa faɗar abin da ba ku sani ba game da Allah?
(69) Ka ce: "Lalle waɗanda suke ƙaga wa Allah ƙarya ba za su rabauta ba."
(70) Jin daɗi ne kawai a cikin duniya, sannan kuma gare Mu ne makomarsu take, sannan Mu ɗanɗana musu azaba mai tsanani saboda abin da suka zamanto suna yi na kafirci



* وَٱتۡلُ عَلَيۡهِمۡ نَبَأَ نُوحٍ إِذۡ قَالَ لِقَوۡمِهِۦ يَٰقَوۡمِ إِن كَانَ كَبُرَ
عَلَيۡكُم مَّقَامِي وَتَذۡكِيرِي بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَعَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلۡتُ
فَأَجۡمِعُوٓاْ أَمۡرَكُمۡ وَشُرَكَآءَكُمۡ ثُمَّ لَا يَكُنۡ أَمۡرُكُمۡ عَلَيۡكُمۡ غُمَّةٗ ثُمَّ
ٱقۡضُوٓاْ إِلَيَّ وَلَا تُنظِرُونِ ٧١ فَإِن تَوَلَّيۡتُمۡ فَمَا سَأَلۡتُكُم مِّنۡ أَجۡرٍۖ
إِنۡ أَجۡرِيَ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِۖ وَأُمِرۡتُ أَنۡ أَكُونَ مِنَ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ٧٢
فَكَذَّبُوهُ فَنَجَّيۡنَٰهُ وَمَن مَّعَهُۥ فِي ٱلۡفُلۡكِ وَجَعَلۡنَٰهُمۡ خَلَٰٓئِفَ
وَأَغۡرَقۡنَا ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَاۖ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُنذَرِينَ
٧٣ ثُمَّ بَعَثۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِۦ رُسُلًا إِلَىٰ قَوۡمِهِمۡ فَجَآءُوهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ
فَمَا كَانُواْ لِيُؤۡمِنُواْ بِمَا كَذَّبُواْ بِهِۦ مِن قَبۡلُۚ كَذَٰلِكَ نَطۡبَعُ عَلَىٰ قُلُوبِ
ٱلۡمُعۡتَدِينَ ٧٤ ثُمَّ بَعَثۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِم مُّوسَىٰ وَهَٰرُونَ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ
وَمَلَإِيْهِۦ بِـَٔايَٰتِنَا فَٱسۡتَكۡبَرُواْ وَكَانُواْ قَوۡمٗا مُّجۡرِمِينَ ٧٥
فَلَمَّا جَآءَهُمُ ٱلۡحَقُّ مِنۡ عِندِنَا قَالُوٓاْ إِنَّ هَٰذَا لَسِحۡرٞ مُّبِينٞ ٧٦
قَالَ مُوسَىٰٓ أَتَقُولُونَ لِلۡحَقِّ لَمَّا جَآءَكُمۡۖ أَسِحۡرٌ هَٰذَاۖ وَلَا يُفۡلِحُ
ٱلسَّٰحِرُونَ ٧٧ قَالُوٓاْ أَجِئۡتَنَا لِتَلۡفِتَنَا عَمَّا وَجَدۡنَا عَلَيۡهِ ءَابَآءَنَا
وَتَكُونَ لَكُمَا ٱلۡكِبۡرِيَآءُ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا نَحۡنُ لَكُمَا بِمُؤۡمِنِينَ ٧٨

(71) Ka kuma karanta musu labarin (Annabi) Nuhu, a lokacin da ya ce da mutanensa: “Ya ku mutanena, idan zamana a cikinku da kuma wa’azin da nake muku da ayoyin Allah sun dame ku, to ni fa ga Allah ne kawai na dogara, sai ku tattara al’amarinku ku kuma (ku kira) abokan tarayyarku, sannan kada al’amarin naku ya zama a ɓoye, sannan ku zartar (da shi) a gare ni, kada kuma ku saurara mini

(72) “To idan kuka ba da baya, to ban tambaye ku wani lada ba; ladana yana ga Allah; an kuwa umarce ni da in kasance cikin Musulmai.”

(73) Sai suka ƙaryata shi, sai Muka tserar da shi da waɗanda suke tare da shi a cikin jirgin ruwa, Muka kuma mayar da su masu maye gurbin (waɗanda suka gabace su), Muka kuma nutsar da waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu. To duba ka ga yadda ƙarshen waɗanda aka yi wa gargaɗi ya kasance

(74) Sannan a bayansa (Annabi Nuhu) Muka aika manzanni zuwa ga mutanensu suka zo musu da (ayoyi) mabayyana, ba su zamanto suna gaskata abin da a da can suke ƙaryata shi ba. Kamar haka ne Muke toshe zukatan masu shisshigi

(75) Sannan daga bayansu Muka aiko Musa da Haruna zuwa ga Fir’auna shi da jama’arsa da ayoyinmu, sai suka yi girman kai suka kuwa zamanto mutane masu laifi

(76) To lokacin da gaskiya ta zo musu daga wurinmu sai suka ce: “Lalle wannan tabbas tsafi ne bayyananne.”

(77) Musa ya ce: “Yanzu kwa riƙa ce wa gaskiya (tsafi) lokacin da ta zo muku? Yanzu wannan ne tsafin, alhali kuwa matsafa ba sa cin nasara?”

(78) Suka ce: “Yanzu ka zo mana ne don ka raba mu da abin da muka sami iyayenmu a kansa, ku kuma (kai da Haruna) ku zamanto ku ne masu girma a bayan ƙasa? Mu kam ba za mu yi imani da ku ba!”

وَقَالَ فِرْعَوْنُ ٱئْتُونِى بِكُلِّ سَٰحِرٍ عَلِيمٍ ﴿٧٩﴾ فَلَمَّا جَآءَ ٱلسَّحَرَةُ
قَالَ لَهُم مُّوسَىٰٓ أَلْقُوا۟ مَآ أَنتُم مُّلْقُونَ ﴿٨٠﴾ فَلَمَّآ أَلْقَوْا۟ قَالَ
مُوسَىٰ مَا جِئْتُم بِهِ ٱلسِّحْرُ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ سَيُبْطِلُهُۥٓ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُصْلِحُ
عَمَلَ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿٨١﴾ وَيُحِقُّ ٱللَّهُ ٱلْحَقَّ بِكَلِمَٰتِهِۦ وَلَوْ كَرِهَ
ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿٨٢﴾ فَمَآ ءَامَنَ لِمُوسَىٰٓ إِلَّا ذُرِّيَّةٌ مِّن قَوْمِهِۦ عَلَىٰ
خَوْفٍ مِّن فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِمْ أَن يَفْتِنَهُمْ ۚ وَإِنَّ فِرْعَوْنَ لَعَالٍ
فِى ٱلْأَرْضِ وَإِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلْمُسْرِفِينَ ﴿٨٣﴾ وَقَالَ مُوسَىٰ يَٰقَوْمِ إِن
كُنتُمْ ءَامَنتُم بِٱللَّهِ فَعَلَيْهِ تَوَكَّلُوٓا۟ إِن كُنتُم مُّسْلِمِينَ ﴿٨٤﴾
فَقَالُوا۟ عَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلْنَا ۚ رَبَّنَا لَا تَجْعَلْنَا فِتْنَةً لِّلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ
﴿٨٥﴾ وَنَجِّنَا بِرَحْمَتِكَ مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٨٦﴾ وَأَوْحَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰ
وَأَخِيهِ أَن تَبَوَّـَٔا لِقَوْمِكُمَا بِمِصْرَ بُيُوتًا وَٱجْعَلُوا۟ بُيُوتَكُمْ
قِبْلَةً وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ ۗ وَبَشِّرِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٨٧﴾ وَقَالَ مُوسَىٰ
رَبَّنَآ إِنَّكَ ءَاتَيْتَ فِرْعَوْنَ وَمَلَأَهُۥ زِينَةً وَأَمْوَٰلًا فِى ٱلْحَيَوٰةِ
ٱلدُّنْيَا رَبَّنَا لِيُضِلُّوا۟ عَن سَبِيلِكَ ۖ رَبَّنَا ٱطْمِسْ عَلَىٰٓ أَمْوَٰلِهِمْ
وَٱشْدُدْ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ فَلَا يُؤْمِنُوا۟ حَتَّىٰ يَرَوُا۟ ٱلْعَذَابَ ٱلْأَلِيمَ ﴿٨٨﴾

(79) Fir’auna kuma ya ce: “Ku zo mini da duk wani ƙwararren matsafi.”
(80) To lokacin da matsafan suka zo, sai Musa ya ce da su: “Ku jefa duk abin da za ku jefa.”
(81) To lokacin da suka jefa (kayan tsafinsu), sai Musa ya ce: “Ai abin da kuka zo da shi tsafi ne; lalle ko Allah zai ɓata shi. Lalle Allah ba Ya gyara aikin maɓarnata
(82)“Allah zai tabbatar da gaskiya da ikonsa ko da kuwa masu manyan laifuka sun ƙi.”
(83) To ba wanda ya yi imani da Musa sai ‘yan samari daga mutanensa don tsoron kada Fir’auna da mutanensa su azabtar da su. Kuma lalle Fir’auna ya tabbata mai girman kai ne a bayan ƙasa. Lalle kuma shi yana cikin maɓarnata
(84) Musa kuma ya ce: “Ya ku mutanena, idan har kun yi imani da Allah, to a gare Shi kawai za ku dogara in kun kasance Musulmai
(85) Sai suka ce: “Ga Allah kaɗai muka dogara. Ya Ubangijinmu, kada ka sanya mu zama fitina ga mutane azzalumai
(86) “Ka kuma tserar da mu da rahamarka daga mutane kafirai.”
(87) Kuma Muka yi wa Musa wahayi shi da ɗan’uwansa cewa: “Ku tanadar wa mutanenku gidaje a Masar, ku kuma sanya gidajenku wurin salla.” Ka kuma yi wa muminai albishir (da samun nasara)
(88) Musa kuma ya ce: “Ya Ubangijinmu, lalle Ka bai wa Fir’auna da mutanensa kayan ado da kuma dukiyoyi a rayuwar duniya; ya Ubangijimu, don su ɓatar (da jama’a) daga hanyarka; ya Ubangijimu, Ka shafe dukiyoyinsu Ka kuma ƙeƙasar da zukatansu ba za su yi imani ba har sai sun ga azaba mai raɗaɗi.”

قَالَ قَدْ أُجِيبَت دَّعْوَتُكُمَا فَٱسْتَقِيمَا وَلَا تَتَّبِعَآنِّ سَبِيلَ
ٱلَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٨٩﴾ ۞ وَجَٰوَزْنَا بِبَنِيٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ٱلْبَحْرَ فَأَتْبَعَهُمْ
فِرْعَوْنُ وَجُنُودُهُۥ بَغْيًا وَعَدْوًا ۖ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَدْرَكَهُ ٱلْغَرَقُ
قَالَ ءَامَنتُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱلَّذِىٓ ءَامَنَتْ بِهِۦ بَنُوٓا۟ إِسْرَٰٓءِيلَ
وَأَنَا۠ مِنَ ٱلْمُسْلِمِينَ ﴿٩٠﴾ ءَآلْـَٰٔنَ وَقَدْ عَصَيْتَ قَبْلُ وَكُنتَ
مِنَ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿٩١﴾ فَٱلْيَوْمَ نُنَجِّيكَ بِبَدَنِكَ لِتَكُونَ لِمَنْ
خَلْفَكَ ءَايَةً ۚ وَإِنَّ كَثِيرًا مِّنَ ٱلنَّاسِ عَنْ ءَايَٰتِنَا لَغَٰفِلُونَ
﴿٩٢﴾ وَلَقَدْ بَوَّأْنَا بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ مُبَوَّأَ صِدْقٍ وَرَزَقْنَٰهُم مِّنَ
ٱلطَّيِّبَٰتِ فَمَا ٱخْتَلَفُوا۟ حَتَّىٰ جَآءَهُمُ ٱلْعِلْمُ ۚ إِنَّ رَبَّكَ يَقْضِى
بَيْنَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُوا۟ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿٩٣﴾ فَإِن كُنتَ فِى شَكٍّ
مِّمَّآ أَنزَلْنَآ إِلَيْكَ فَسْـَٔلِ ٱلَّذِينَ يَقْرَءُونَ ٱلْكِتَٰبَ مِن
قَبْلِكَ ۚ لَقَدْ جَآءَكَ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُمْتَرِينَ ﴿٩٤﴾
وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَتَكُونَ مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ
﴿٩٥﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ حَقَّتْ عَلَيْهِمْ كَلِمَتُ رَبِّكَ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿٩٦﴾
وَلَوْ جَآءَتْهُمْ كُلُّ ءَايَةٍ حَتَّىٰ يَرَوُا۟ ٱلْعَذَابَ ٱلْأَلِيمَ ﴿٩٧﴾

(89) (Allah) Ya ce: “Haƙiƙa an amsa addu’arku, sai ku tsaya ƙyam (a kan tafarkinku), kada kuwa ku bi hanyar waɗanda ba sa sanin (gaskiya).”
(90) Muka kuma ƙetarar da Banu Isra’ila kogi, sai Fir’auna ya bi su shi da rundunarsa don zalunci da ta’addanci, har sai lokacin da nutsewa ta riske shi sai ya ce: “Na yi imani cewa babu wani abin bauta sai wanda Banu Isra’ila suka yi imani da shi, kuma ni ina cikin Musulmai.”
(91) Sai yanzu kuma, bayan da can ka yi ta saɓo, ka kuma kasance cikin masu ɓarna?
(92) To a yau kam za Mu tserar da gangar jikinka don ka zamanto aya ga na bayanka. Lalle kuwa yawancin mutane masu gafala ne ga lura da ayoyinmu
(93) Haƙiƙa Mun sanya Banu Isra’ila a kyakkyawan matsayi na gaskiya, Muka kuma arzuta su da abubuwa daɗaɗa na halal, to kawunansu ba su tashi rabuwa ba har sai lokacin da ilimi ya zo musu. Lalle Ubangijinka zai yi hukunci tsakaninsu ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna saɓani a kansa
(94) To idan kana tababa[1] game da abin da Muka saukar maka to sai ka tambayi waɗanda suke karanta littafi gabaninka. Haƙiƙa gaskiya ta zo maka daga Ubangijinka; to kada ka zama daga cikin masu kokwanto
(95) Lalle kuma kada ka kasance daga cikin waɗanda suka ƙaryata ayoyin Allah, sai ka zamo daga asararru
(96) Lalle waɗanda kalmar Ubangijinka ta tabbata a kansu (ta zamansu ‘yan wuta) ba za su yi imani ba
(97) Ko da kuwa dukkanin ayoyi sun zo musu har sai sun ga azaba mai raɗaɗi

(1) Annabi ( ) ba taɓa yin tababa ba game da wahayin da Allah ( ) ya yi masa, amma abin nufi a nan shi ne kafa hujja ga Ahlulkitab a kan gaskiyar Annabi ( ).

فَلَوْلَا كَانَتْ قَرْيَةٌ ءَامَنَتْ فَنَفَعَهَآ إِيمَٰنُهَآ إِلَّا قَوْمَ يُونُسَ
لَمَّآ ءَامَنُوا۟ كَشَفْنَا عَنْهُمْ عَذَابَ ٱلْخِزْىِ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا
وَمَتَّعْنَٰهُمْ إِلَىٰ حِينٍ ﴿٩٨﴾ وَلَوْ شَآءَ رَبُّكَ لَءَامَنَ مَن فِى ٱلْأَرْضِ
كُلُّهُمْ جَمِيعًا ۚ أَفَأَنتَ تُكْرِهُ ٱلنَّاسَ حَتَّىٰ يَكُونُوا۟ مُؤْمِنِينَ
﴿٩٩﴾ وَمَا كَانَ لِنَفْسٍ أَن تُؤْمِنَ إِلَّا بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۚ وَيَجْعَلُ ٱلرِّجْسَ
عَلَى ٱلَّذِينَ لَا يَعْقِلُونَ ﴿١٠٠﴾ قُلِ ٱنظُرُوا۟ مَاذَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ ۚ وَمَا تُغْنِى ٱلْـَٔايَٰتُ وَٱلنُّذُرُ عَن قَوْمٍ لَّا يُؤْمِنُونَ
﴿١٠١﴾ فَهَلْ يَنتَظِرُونَ إِلَّا مِثْلَ أَيَّامِ ٱلَّذِينَ خَلَوْا۟ مِن قَبْلِهِمْ ۚ
قُلْ فَٱنتَظِرُوٓا۟ إِنِّى مَعَكُم مِّنَ ٱلْمُنتَظِرِينَ ﴿١٠٢﴾ ثُمَّ نُنَجِّى
رُسُلَنَا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ كَذَٰلِكَ ۖ حَقًّا عَلَيْنَا نُنجِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١٠٣﴾
قُلْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِن كُنتُمْ فِى شَكٍّ مِّن دِينِى فَلَآ أَعْبُدُ ٱلَّذِينَ
تَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَٰكِنْ أَعْبُدُ ٱللَّهَ ٱلَّذِى يَتَوَفَّىٰكُمْ ۖ وَأُمِرْتُ
أَنْ أَكُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١٠٤﴾ وَأَنْ أَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفًا
وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿١٠٥﴾ وَلَا تَدْعُ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا
يَنفَعُكَ وَلَا يَضُرُّكَ ۖ فَإِن فَعَلْتَ فَإِنَّكَ إِذًا مِّنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٠٦﴾

(98) Babu wasu mutane na wata alkarya da suka yi imani, sannan imaninsu ya amfane su, sai fa mutanen Yunusa, lokacin da suka yi imani sai Muka yaye musu azabar wulakanci a rayuwar duniya, Muka kuma jiyar da su dadi har zuwa wani lokaci (iyakantacce)

(99) Da Ubangijinka Ya ga dama lalle da duk wadanda suke bayan kasa sun yi imani gaba dayansu. Shin kai ne za ka tilasa wa mutane har su zama muminai?

(100) Ba zai yiwu wani rai ya yi imani ba sai da izinin Allah. Yana kuma sanya azaba ne a kan wadanda ba sa hankalta

(101) Ka ce: "Ku yi tunanin abubuwan da suke cikin sammai da kasa." Ayoyi kuwa da masu gargadi ba sa wadatar da mutanen da ba sa yin imani

(102) Ai ba abin da suke saurare sai irin azabar da ta sami wadanda suka wuce gabaninsu. Ka ce: "Sai ku saurara, lalle ni ma ina tare da ku cikin masu sauraro."

(103) Sannan Muka rika tserar da manzanninmu da wadanda suka yi imani da su. Kamar haka ne ya zama lalle a kanmu Mu tserar da muminai

(104) Ka ce: "Ya ku mutane, idan kun kasance cikin kokwanto game da addinina, to ba zan bauta wa wadanda kuke bauta wa ba Allah ba, sai dai ni zan bauta wa Allah ne wanda Yake karbar rayukanku, an kuma umarce ni da in zama cikin muminai

(105) "Kuma (an umarce ni) da cewa: 'Ka tsai da fuskarka ga addinin Allah wanda ya karkace wa barna, kada kuma ka kasance cikin mushirikai

(106) "Kada kuma ka bauta wa wani ba Allah ba, abin da ba zai amfane ka ba, ba kuma zai cuce ka ba; to idan kuwa ka aikata haka to lalle daga sannan ka zama cikin azzalumai.'"

وَإِن يَمْسَسْكَ ٱللَّهُ بِضُرٍّ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَ ۖ وَإِن يُرِدْكَ
بِخَيْرٍ فَلَا رَآدَّ لِفَضْلِهِۦ ۚ يُصِيبُ بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ ۚ
وَهُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٠٧﴾ قُلْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدْ جَآءَكُمُ ٱلْحَقُّ
مِن رَّبِّكُمْ ۖ فَمَنِ ٱهْتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهْتَدِى لِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَن ضَلَّ
فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيْهَا ۖ وَمَآ أَنَا۠ عَلَيْكُم بِوَكِيلٍ ﴿١٠٨﴾ وَٱتَّبِعْ مَا يُوحَىٰٓ
إِلَيْكَ وَٱصْبِرْ حَتَّىٰ يَحْكُمَ ٱللَّهُ ۚ وَهُوَ خَيْرُ ٱلْحَٰكِمِينَ ﴿١٠٩﴾

سُورَةُ هُودٍ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ


الٓر ۚ كِتَٰبٌ أُحْكِمَتْ ءَايَٰتُهُۥ ثُمَّ فُصِّلَتْ مِن لَّدُنْ حَكِيمٍ خَبِيرٍ ﴿١﴾
أَلَّا تَعْبُدُوٓا۟ إِلَّا ٱللَّهَ ۚ إِنَّنِى لَكُم مِّنْهُ نَذِيرٌ وَبَشِيرٌ ﴿٢﴾ وَأَنِ ٱسْتَغْفِرُوا۟
رَبَّكُمْ ثُمَّ تُوبُوٓا۟ إِلَيْهِ يُمَتِّعْكُم مَّتَٰعًا حَسَنًا إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى وَيُؤْتِ
كُلَّ ذِى فَضْلٍ فَضْلَهُۥ ۖ وَإِن تَوَلَّوْا۟ فَإِنِّىٓ أَخَافُ عَلَيْكُمْ عَذَابَ يَوْمٍ
كَبِيرٍ ﴿٣﴾ إِلَى ٱللَّهِ مَرْجِعُكُمْ ۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٤﴾ أَلَآ إِنَّهُمْ
يَثْنُونَ صُدُورَهُمْ لِيَسْتَخْفُوا۟ مِنْهُ ۚ أَلَا حِينَ يَسْتَغْشُونَ ثِيَابَهُمْ
يَعْلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعْلِنُونَ ۚ إِنَّهُۥ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿٥﴾

(107) Idan Allah Ya ɗora maka wata cuta to ba mai yaye maka ita sai shi; idan kuma Ya nufe ka da alheri to ba mai juyar da falalarsa. Yana bayar da shi ga waɗanda Ya ga dama daga bayinsa. Shi ne kuma Mai gafara, Mai jin ƙai
(108) Ka ce: "Ya ku mutane, haƙiƙa gaskiya ta zo muku daga Ubangijinku; duk wanda ya shiriya to ya shiriya ne don kansa; wanda kuma ya ɓace to lalle ya ɓace don kansa ne; ni kuwa ba wakili ne a kanku ba."
(109) Kuma ka bi abin da aka yi maka wahayinsa, ka kuma yi haƙuri har sai Allah Ya yi hukunci. Shi ne kuwa Fiyayyen masu hukunci

Sura Hud

(1) ALIF LAM RA[1]. (Wannan) Littafi ne da aka kyautata ayoyinsa sannan aka bayyana su filla-filla, daga wurin Mai hikima, Masani
(2) Da cewa kada ku bauta wa kowa sai Allah. (Ka ce): "Lalle ni mai yi muku gargaɗi ne mai albishir daga gare Shi (Allah)
(3) "Kuma da cewa, ku nemi gafarar Ubangijinku sannan ku tuba gare Shi, zai jiyar da ku daɗi, kyakkyawar jiyarwa zuwa wani lokaci ƙayyadadde, Ya kuma bai wa duk wani wanda Ya yi abin kirki (sakamakon) kirkinsa. Idan kuwa kuka ba da baya, to lalle ni ina jiye muku tsoron azabar wani yini mai girma
(4) "Zuwa ga Allah ne makomarku; Shi kuwa Mai iko ne a kan komai."
(5) Ku saurara! Lalle su suna karkatar da ƙirazansu don su ɓoye masa (Allah). Ku saurara! Ai lokacin da suke lulluɓa da tufafinsu Yana sane da abin da suke ɓoyewa da kuma abin da suke bayyanawa. Lalle Shi (Allah) Masanin abin da yake cikin zukata ne

(1) Duba Suratul Baƙara aya ta 1, hashiya ta 8.


* وَمَا مِن دَآبَّةٍ فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ رِزۡقُهَا وَيَعۡلَمُ
مُسۡتَقَرَّهَا وَمُسۡتَوۡدَعَهَاۚ كُلّٞ فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٖ ٦ وَهُوَ
ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ وَكَانَ
عَرۡشُهُۥ عَلَى ٱلۡمَآءِ لِيَبۡلُوَكُمۡ أَيُّكُمۡ أَحۡسَنُ عَمَلٗاۗ وَلَئِن
قُلۡتَ إِنَّكُم مَّبۡعُوثُونَ مِنۢ بَعۡدِ ٱلۡمَوۡتِ لَيَقُولَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ
إِنۡ هَٰذَآ إِلَّا سِحۡرٞ مُّبِينٞ ٧ وَلَئِنۡ أَخَّرۡنَا عَنۡهُمُ ٱلۡعَذَابَ إِلَىٰٓ
أُمَّةٖ مَّعۡدُودَةٖ لَّيَقُولُنَّ مَا يَحۡبِسُهُۥٓۗ أَلَا يَوۡمَ يَأۡتِيهِمۡ لَيۡسَ
مَصۡرُوفًا عَنۡهُمۡ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ
٨ وَلَئِنۡ أَذَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ مِنَّا رَحۡمَةٗ ثُمَّ نَزَعۡنَٰهَا مِنۡهُ إِنَّهُۥ
لَيَـُٔوسٞ كَفُورٞ ٩ وَلَئِنۡ أَذَقۡنَٰهُ نَعۡمَآءَ بَعۡدَ ضَرَّآءَ
مَسَّتۡهُ لَيَقُولَنَّ ذَهَبَ ٱلسَّيِّـَٔاتُ عَنِّيٓۚ إِنَّهُۥ لَفَرِحٞ فَخُورٌ
١٠ إِلَّا ٱلَّذِينَ صَبَرُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُم
مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٞ كَبِيرٞ ١١ فَلَعَلَّكَ تَارِكُۢ بَعۡضَ مَا يُوحَىٰٓ إِلَيۡكَ
وَضَآئِقُۢ بِهِۦ صَدۡرُكَ أَن يَقُولُواْ لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡهِ كَنزٌ أَوۡ جَآءَ
مَعَهُۥ مَلَكٌۚ إِنَّمَآ أَنتَ نَذِيرٞۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ وَكِيلٌ ١٢

(6) Kuma babu wata dabba a ban ƙasa face arzikinta yana hannun Allah, kuma Yana sane da matabbatarta da ma'ajiyarta[1]. Dukkanin wannan yana nan a cikin littafi mabayyani (shi ne Lauhul Mahafuzu)

(7) Shi ne kuma wanda Ya halicci sammai da ƙasa cikin kwana shida, Al'arshinsa kuwa ya kasance a kan ruwa, don Ya jarraba ku a cikinku wa ya fi kyakkyawan aiki. Kuma tabbas idan ka ce (da su): "Lalle za a tashe ku bayan mutuwa," tabbas kafirai za su ce: "Ai wannan ba wani abu ba ne sai tsafi mabayyani."

(8) Kuma tabbas da Mun jinkirta musu azaba zuwa wani lokaci ƙayyadadde, lalle za su ce: "Me ya tsare ta?" Ku saurara! Ranar da za ta zo musu ba za a kawar da ita daga kansu ba, kuma abin da suke yi wa izgili zai tabbata a kansu

(9) Kuma tabbas idan Muka ɗanɗana wa mutum wata rahama daga gare Mu sannan Muka karɓe ta daga gare shi, lalle shi mai yawan yanke ƙauna ne, mai kuma yawan kafirci

(10) Lalle kuma idan Muka ɗanɗana masa daɗi bayan ya sha wahala da ta same shi, tabbas zai riƙa cewa: "Ai munanan (abubuwa) sun bar ni." Lalle shi mai farin ciki ne mai yawan alfahari

(11) Sai dai waɗanda suka yi haƙuri suka kuma yi aiki nagari, waɗannan suna da gafara da kuma lada mai girma

(12) To yanzu za ka bar wani abu daga abin da ake yi maka wahayi da shi, kuma zuciyarka za ta ƙuntata da shi don kawai za su ce: "Me ya hana a saukar masa da wata taska, ko kuma wani mala'ika ya zo tare da shi?" Kai dai mai gargaɗi ne kawai. Allah kuma Wakili ne a kan komai

(1) Watau ya san wurin zamansu da wurin tafiye-tafiyensu, ya san inda za su mutu a binne su.

أَمْ يَقُولُونَ ٱفْتَرَىٰهُ ۖ قُلْ فَأْتُوا۟ بِعَشْرِ سُوَرٍ مِّثْلِهِۦ مُفْتَرَيَٰتٍ
وَٱدْعُوا۟ مَنِ ٱسْتَطَعْتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿١٣﴾
فَإِلَّمْ يَسْتَجِيبُوا۟ لَكُمْ فَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّمَآ أُنزِلَ بِعِلْمِ ٱللَّهِ وَأَن
لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ فَهَلْ أَنتُم مُّسْلِمُونَ ﴿١٤﴾ مَن كَانَ يُرِيدُ ٱلْحَيَوٰةَ
ٱلدُّنْيَا وَزِينَتَهَا نُوَفِّ إِلَيْهِمْ أَعْمَٰلَهُمْ فِيهَا وَهُمْ فِيهَا
لَا يُبْخَسُونَ ﴿١٥﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَيْسَ لَهُمْ فِى ٱلْءَاخِرَةِ إِلَّا
ٱلنَّارُ ۖ وَحَبِطَ مَا صَنَعُوا۟ فِيهَا وَبَٰطِلٌ مَّا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٦﴾
أَفَمَن كَانَ عَلَىٰ بَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّهِۦ وَيَتْلُوهُ شَاهِدٌ مِّنْهُ وَمِن قَبْلِهِۦ
كِتَٰبُ مُوسَىٰٓ إِمَامًا وَرَحْمَةً ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ يُؤْمِنُونَ بِهِۦ ۚ وَمَن يَكْفُرْ
بِهِۦ مِنَ ٱلْأَحْزَابِ فَٱلنَّارُ مَوْعِدُهُۥ ۚ فَلَا تَكُ فِى مِرْيَةٍ مِّنْهُ ۚ إِنَّهُ
ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّكَ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿١٧﴾ وَمَنْ
أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ يُعْرَضُونَ عَلَىٰ
رَبِّهِمْ وَيَقُولُ ٱلْأَشْهَٰدُ هَٰٓؤُلَآءِ ٱلَّذِينَ كَذَبُوا۟ عَلَىٰ رَبِّهِمْ ۚ
أَلَا لَعْنَةُ ٱللَّهِ عَلَى ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٨﴾ ٱلَّذِينَ يَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ
ٱللَّهِ وَيَبْغُونَهَا عِوَجًا وَهُم بِٱلْءَاخِرَةِ هُمْ كَٰفِرُونَ ﴿١٩﴾

(13) A'a, ko cewa suka yi: "Ya ƙirƙire shi ne?" Ka ce: "Ku kawo sura goma kamarsa ƙagaggu, kuma ku kira duk wanda za ku iya wanda ba Allah ba (ya taimake ku) in kun kasance masu gaskiya."
(14) To idan ba su amsa muku ba, to ku tabbatar cewa lalle an saukar da shi ne (Alƙur'ani) da sanin Allah, kuma babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, To shin yanzu za ku miƙa wuya?
(15) Waɗanda suke nufin rayuwar duniya da ƙawace-ƙawacenta, to za Mu ba su cikakken sakamakon ayyukansu a cikinta, kuma ba za a tauye musu (komai ba)
(16) Waɗannan su ne waɗanda ba su da komai a lahira sai wuta; kuma abin da suka aikata a cikinta (duniyar) ya rushe, kuma abin da suke aikatawa ya lalace
(17) Shin yanzu wanda yake a kan hujja daga Ubangijinsa, kuma wani mai ba da shaida yana biye da shi (Alƙur'ani); a gabaninsa kuma akwai Littafin (Annabi) Musa (wanda yake) abin koyi ne, kuma rahama ne, (zai yi daidai da wanda ba haka ba)? Waɗannan suna yin imani da shi. Daga sauran ƙungiyoyi kuma duk wanda ya kafirce da shi, to fa wuta ce makomarsa. Don haka kada ka kasance cikin kokwanto game da shi (Alƙur'ani). Lalle shi gaskiya ne daga Ubangijika yake, sai dai kuma yawancin mutane ba sa yin imani
(18) Kuma ba wanda ya fi zalunci kamar wanda ya ƙirƙira wa Allah ƙarya. Waɗannan za a kawo su a gaban Ubangijinsu, shaidu kuma (wato mala'iku) su ce: "Waɗannan su ne suka yi wa Ubangijinsu ƙarya. Ku saurara, la'anar Allah ta tabbata a kan azzalumai
(19) "Waɗanda suke hana bin hanyar Allah, suna kuma son ta a karkace; kuma su ne masu kafircewa da ranar lahira."

أُولَٰئِكَ لَمْ يَكُونُوا۟ مُعْجِزِينَ فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا كَانَ لَهُم مِّن دُونِ
ٱللَّهِ مِنْ أَوْلِيَآءَ ۘ يُضَٰعَفُ لَهُمُ ٱلْعَذَابُ ۚ مَا كَانُوا۟ يَسْتَطِيعُونَ
ٱلسَّمْعَ وَمَا كَانُوا۟ يُبْصِرُونَ ﴿٢٠﴾ أُولَٰئِكَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓا۟
أَنفُسَهُمْ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ﴿٢١﴾ لَا جَرَمَ أَنَّهُمْ
فِى ٱلْءَاخِرَةِ هُمُ ٱلْأَخْسَرُونَ ﴿٢٢﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟
ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَأَخْبَتُوٓا۟ إِلَىٰ رَبِّهِمْ أُولَٰئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ ۖ
هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿٢٣﴾ ۞ مَثَلُ ٱلْفَرِيقَيْنِ كَٱلْأَعْمَىٰ وَٱلْأَصَمِّ
وَٱلْبَصِيرِ وَٱلسَّمِيعِ ۚ هَلْ يَسْتَوِيَانِ مَثَلًا ۚ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ
﴿٢٤﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوْمِهِۦٓ إِنِّى لَكُمْ نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿٢٥﴾
أَن لَّا تَعْبُدُوٓا۟ إِلَّا ٱللَّهَ ۖ إِنِّىٓ أَخَافُ عَلَيْكُمْ عَذَابَ يَوْمٍ أَلِيمٍ ﴿٢٦﴾
فَقَالَ ٱلْمَلَأُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِن قَوْمِهِۦ مَا نَرَىٰكَ إِلَّا بَشَرًا مِّثْلَنَا
وَمَا نَرَىٰكَ ٱتَّبَعَكَ إِلَّا ٱلَّذِينَ هُمْ أَرَاذِلُنَا بَادِىَ ٱلرَّأْىِ
وَمَا نَرَىٰ لَكُمْ عَلَيْنَا مِن فَضْلٍ بَلْ نَظُنُّكُمْ كَٰذِبِينَ ﴿٢٧﴾
قَالَ يَٰقَوْمِ أَرَءَيْتُمْ إِن كُنتُ عَلَىٰ بَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّى وَءَاتَىٰنِى رَحْمَةً مِّنْ
عِندِهِۦ فَعُمِّيَتْ عَلَيْكُمْ ۚ أَنُلْزِمُكُمُوهَا وَأَنتُمْ لَهَا كَٰرِهُونَ ﴿٢٨﴾

(20) Wadannan ba su zamo masu gagara ba a bayan ƙasa, kuma ba su da masu jiɓintar lamarinsu wadanda ba Allah ba, (kuma) za a ninka musu azaba. Ba su kasance sun iya jin (gaskiya) ba, ba su kuma zamanto masu iya ganin (ta) ba

(21) Wadannan su ne wadanda suka yi asarar kawunansu. Abin da suke ƙirƙira kuma ya ɓace musu

(22) Ba shakka lalle su ne suka fi asara a lahira

(23) Lalle wadanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, suka kuma ƙasƙantar da kansu ga Ubangijinsu to wadannan su ne 'yan Aljanna, su masu dawwama ne a cikinta

(24) Misalin jama'ar nan guda biyu (mumini da kafiri) kamar makaho ne da kurma da kuma mai gani da mai ji. Shin ga misali za su zama daidai kuwa? To me ya sa ba za ku wa'azantu ba?

(25) Haƙiƙa kuma Mun aiko Nuhu zuwa ga mutanensa (ya ce da su): "Lalle ni mai gargadi bayyananne ne a gare ku

(26) "Cewa kada ku bauta wa (kowa) sai Allah. Lalle ni ina jiye muku tsoron azabar wata rana mai radadi."

(27) Sai manya-manya daga cikin mutanensa, wadanda suka kafirta suka ce (da shi): "Mu fa mun ɗauke ka kawai mutum ne kamarmu, kuma ba ma ganin wani ya bi ka in ban da wulakantattun cikinmu gidadawa. Kuma ba ma ganin ku da wani fifiko a kanmu; kai muna ma tsammanin ku maƙaryata ne."

(28) (Annabi Nuhu) ya ce: "Ya ku mutanena, ku ba ni labari, yanzu idan na zamanto ina riƙe da hujja daga Ubangijina, Ya kuma ba ni wata rahama daga gare Shi, sai aka ɓoye muku ita, yanzu ma tilasta muku ita, alhali kuwa kuna ƙin ta?

وَيَٰقَوْمِ لَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ مَالًا ۖ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ وَمَآ أَنَا۠
بِطَارِدِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ ۚ إِنَّهُم مُّلَٰقُوا۟ رَبِّهِمْ وَلَٰكِنِّىٓ أَرَىٰكُمْ قَوْمًا
تَجْهَلُونَ ﴿٢٩﴾ وَيَٰقَوْمِ مَن يَنصُرُنِى مِنَ ٱللَّهِ إِن طَرَدتُّهُمْ ۚ أَفَلَا
تَذَكَّرُونَ ﴿٣٠﴾ وَلَآ أَقُولُ لَكُمْ عِندِى خَزَآئِنُ ٱللَّهِ وَلَآ
أَعْلَمُ ٱلْغَيْبَ وَلَآ أَقُولُ إِنِّى مَلَكٌ وَلَآ أَقُولُ لِلَّذِينَ تَزْدَرِىٓ
أَعْيُنُكُمْ لَن يُؤْتِيَهُمُ ٱللَّهُ خَيْرًا ۖ ٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا فِىٓ أَنفُسِهِمْ ۖ إِنِّىٓ
إِذًا لَّمِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٣١﴾ قَالُوا۟ يَٰنُوحُ قَدْ جَٰدَلْتَنَا فَأَكْثَرْتَ جِدَٰلَنَا
فَأْتِنَا بِمَا تَعِدُنَآ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿٣٢﴾ قَالَ إِنَّمَا
يَأْتِيكُم بِهِ ٱللَّهُ إِن شَآءَ وَمَآ أَنتُم بِمُعْجِزِينَ ﴿٣٣﴾ وَلَا يَنفَعُكُمْ
نُصْحِىٓ إِنْ أَرَدتُّ أَنْ أَنصَحَ لَكُمْ إِن كَانَ ٱللَّهُ يُرِيدُ أَن
يُغْوِيَكُمْ ۚ هُوَ رَبُّكُمْ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٣٤﴾ أَمْ يَقُولُونَ ٱفْتَرَىٰهُ ۖ
قُلْ إِنِ ٱفْتَرَيْتُهُۥ فَعَلَىَّ إِجْرَامِى وَأَنَا۠ بَرِىٓءٌ مِّمَّا تُجْرِمُونَ
﴿٣٥﴾ وَأُوحِىَ إِلَىٰ نُوحٍ أَنَّهُۥ لَن يُؤْمِنَ مِن قَوْمِكَ إِلَّا مَن قَدْ ءَامَنَ
فَلَا تَبْتَئِسْ بِمَا كَانُوا۟ يَفْعَلُونَ ﴿٣٦﴾ وَٱصْنَعِ ٱلْفُلْكَ بِأَعْيُنِنَا
وَوَحْيِنَا وَلَا تُخَٰطِبْنِى فِى ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓا۟ ۖ إِنَّهُم مُّغْرَقُونَ ﴿٣٧﴾



(29) “Kuma ya ku mutanena, ba na tambayar ku wata dukiya a kansa (kiran); ladana a wurin Allah kawai yake. Ni kuwa ba zan kori waɗanda suka yi imani ba. Lalle su masu saduwa ne da Ubangijinsu, sai dai ni ina ganin ku mutane ne da kuke jahiltar (gaskiya).”
(30) “Ya ku mutanena, wa zai kare ni daga Allah idan na kore su? Me ya sa ne ba kwa wa’azantuwa?
(31) “Ba kuma zan ce da ku ina da taskokin Allah ba, ban kuma san gaibu ba, kuma ba zan ce lalle ni mala’ika ne ba, ba kuma zan ce wa waɗanda idanuwanku suke wulaƙantawa, Allah ba zai ba su wani alheri ba. Allah ne Ya fi sanin abin da yake zukatansu. Idan na yi haka, to lalle na zamanto daga cikin azzalumai.”
(32) Suka ce: “Ya Nuhu, haƙiƙa ka ja da mu, ka kuma yawaita jayayya da mu; to sai ka zo mana da abin da kake yi mana alƙawari da shi (na narko) in ka zamo daga masu gaskiya.”
(33) Ya ce: “Ai Allah ne zai zo muku da shi idan Ya ga dama, ku kuma ba za ku gagara ba
(34) “Nasihata kuma ba za ta amfane ku ba - ko da na yi nufin yi muku nasihar - idan har da ma can Allah Yana nufin Ya ɓatar da ku. Shi ne Ubangijinku, kuma wurinsa za ku koma.”
(35) A’a, ko dai cewa suke: “Kagar sa ya yi?” (wato Alƙur’ani) Ka ce: “Idan ƙagar sa na yi, to alhakin ƙagena yana kaina ne, ni kuma ba ruwana da laifin abin da kuke tabkawa.”
(36) Aka kuma yi wa Nuhu wahayi cewa: “Ba wanda zai yi imani daga mutanenka sai waɗanda suka riga suka yi. To kada ka yi baƙin ciki game da abin da suke aikatawa
(37) “Ka kuma sassaƙa jirgin ruwa a kan idanunmu da koyarwarmu. Kada kuma ka yi Mini maganar komai game da kafirai. Lalle su nutsar da su za a yi.”

وَيَصۡنَعُ ٱلۡفُلۡكَ وَكُلَّمَا مَرَّ عَلَيۡهِ مَلَأٞ مِّن قَوۡمِهِۦ سَخِرُواْ مِنۡهُۚ
قَالَ إِن تَسۡخَرُواْ مِنَّا فَإِنَّا نَسۡخَرُ مِنكُمۡ كَمَا تَسۡخَرُونَ
﴿٣٨﴾ فَسَوۡفَ تَعۡلَمُونَ مَن يَأۡتِيهِ عَذَابٞ يُخۡزِيهِ وَيَحِلُّ عَلَيۡهِ عَذَابٞ
مُّقِيمٞ ﴿٣٩﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَ أَمۡرُنَا وَفَارَ ٱلتَّنُّورُ قُلۡنَا ٱحۡمِلۡ فِيهَا
مِن كُلّٖ زَوۡجَيۡنِ ٱثۡنَيۡنِ وَأَهۡلَكَ إِلَّا مَن سَبَقَ عَلَيۡهِ ٱلۡقَوۡلُ
وَمَنۡ ءَامَنَۚ وَمَآ ءَامَنَ مَعَهُۥٓ إِلَّا قَلِيلٞ ﴿٤٠﴾ ۞ وَقَالَ ٱرۡكَبُواْ
فِيهَا بِسۡمِ ٱللَّهِ مَجۡرٖىٰهَا وَمُرۡسَىٰهَآۚ إِنَّ رَبِّي لَغَفُورٞ رَّحِيمٞ
﴿٤١﴾ وَهِيَ تَجۡرِي بِهِمۡ فِي مَوۡجٖ كَٱلۡجِبَالِ وَنَادَىٰ نُوحٌ ٱبۡنَهُۥ
وَكَانَ فِي مَعۡزِلٖ يَٰبُنَيَّ ٱرۡكَب مَّعَنَا وَلَا تَكُن مَّعَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ﴿٤٢﴾
قَالَ سَـَٔاوِيٓ إِلَىٰ جَبَلٖ يَعۡصِمُنِي مِنَ ٱلۡمَآءِۚ قَالَ لَا عَاصِمَ ٱلۡيَوۡمَ
مِنۡ أَمۡرِ ٱللَّهِ إِلَّا مَن رَّحِمَۚ وَحَالَ بَيۡنَهُمَا ٱلۡمَوۡجُ فَكَانَ مِنَ
ٱلۡمُغۡرَقِينَ ﴿٤٣﴾ وَقِيلَ يَٰٓأَرۡضُ ٱبۡلَعِي مَآءَكِ وَيَٰسَمَآءُ أَقۡلِعِي
وَغِيضَ ٱلۡمَآءُ وَقُضِيَ ٱلۡأَمۡرُ وَٱسۡتَوَتۡ عَلَى ٱلۡجُودِيِّۖ وَقِيلَ
بُعۡدٗا لِّلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٤٤﴾ وَنَادَىٰ نُوحٞ رَّبَّهُۥ فَقَالَ رَبِّ إِنَّ ٱبۡنِي
مِنۡ أَهۡلِي وَإِنَّ وَعۡدَكَ ٱلۡحَقُّ وَأَنتَ أَحۡكَمُ ٱلۡحَٰكِمِينَ ﴿٤٥﴾

(38) Ya kuma rika sassaka jirgin, duk sanda kuma wasu manya daga mutanensa suka wuce ta wajensa sai su rika yi masa ba'a. Ya ce: "Idan kun yi mana ba'a, to lalle mu ma fa (wata rana) za mu yi muku ba'ar kamar yadda kuke mana (yanzu)
(39) "To ba da daɗewa ba za ku san wanda azaba mai kunyatarwa za ta zo masa, kuma wata azaba madawwamiya ta sauka a kansa."
(40) Har dai zuwa lokacin da umarninmu ya zo, kuma tanderu ya ɓuɓbugo da ruwa, Muka ce: "Ka ɗauki ma'aurata bibbiyu daga kowace (halitta) a cikinsa (jirgin) haɗe da iyalanka in ban da wanda maganar (halakar da shi) ta gabata a kansa, kuma (ka ɗauki) waɗanda suka yi imani." Ba kuwa waɗanda suka yi imani da shi sai 'yan tsirari
(41) Ya kuma ce: "Ku shiga cikinsa, da sunan Allah ne tafiyarsa da kuma tsayawarsa. Lalle Ubangijina Mai gafara ne, Mai rahama."
(42) Shi kuma (jirgin) yana tafiya da su cikin raƙuman ruwa kamar duwatsu, Nuhu kuwa sai ya kirawo ɗansa alhalin ya kasance a ware waje ɗaya (ya ce): "Kai ɗana, ka hawo mana tare da mu, kada ka zama tare da kafirai."
(43) (Ɗan) ya ce: "Ai zan fake a wani dutse wanda zai kare ni daga ruwan." (Annabi Nuhu) ya ce: "Yau kam babu mai kariya daga al'amarin Allah sai dai wanda Ya yi wa rahama kawai." Sai raƙumin ruwa ya shiga tsakaninsu, ya zamanto cikin waɗanda aka nutsar (a cikin ruwa)
(44) Aka ce: "Ke ƙasa, ki haɗiye ruwanki, ke kuma sama ki riƙe ruwanki, aka kuwa ƙafar da ruwan, kuma aka gama al'amarin, (jirgin) kuma ya tsaya a kan (dutsen) Judi; aka kuma ce: Halaka ta tabbata ga mutane azzalumai."
(45) Nuhu kuma ya kira Ubangijinsa sai ya ce: "Ya Ubangijina, lalle ɗana yana daga iyalina, lalle kuma alƙawarinka gaskiya ne, kuma Kai ne Ka fi masu hukunci iya hukunci."

قَالَ يَٰنُوحُ إِنَّهُۥ لَيْسَ مِنْ أَهْلِكَ ۖ إِنَّهُۥ عَمَلٌ غَيْرُ صَٰلِحٍ ۖ فَلَا تَسْـَٔلْنِ
مَا لَيْسَ لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ ۖ إِنِّىٓ أَعِظُكَ أَن تَكُونَ مِنَ ٱلْجَٰهِلِينَ
﴿٤٦﴾ قَالَ رَبِّ إِنِّىٓ أَعُوذُ بِكَ أَنْ أَسْـَٔلَكَ مَا لَيْسَ لِى بِهِۦ عِلْمٌ ۖ وَإِلَّا
تَغْفِرْ لِى وَتَرْحَمْنِىٓ أَكُن مِّنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿٤٧﴾ قِيلَ يَٰنُوحُ
ٱهْبِطْ بِسَلَٰمٍ مِّنَّا وَبَرَكَٰتٍ عَلَيْكَ وَعَلَىٰٓ أُمَمٍ مِّمَّن مَّعَكَ ۚ
وَأُمَمٌ سَنُمَتِّعُهُمْ ثُمَّ يَمَسُّهُم مِّنَّا عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٤٨﴾ تِلْكَ
مِنْ أَنۢبَآءِ ٱلْغَيْبِ نُوحِيهَآ إِلَيْكَ ۖ مَا كُنتَ تَعْلَمُهَآ أَنتَ
وَلَا قَوْمُكَ مِن قَبْلِ هَٰذَا ۖ فَٱصْبِرْ ۖ إِنَّ ٱلْعَٰقِبَةَ لِلْمُتَّقِينَ ﴿٤٩﴾
وَإِلَىٰ عَادٍ أَخَاهُمْ هُودًا ۚ قَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ
إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥ ۖ إِنْ أَنتُمْ إِلَّا مُفْتَرُونَ ﴿٥٠﴾ يَٰقَوْمِ لَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ
أَجْرًا ۖ إِنْ أَجْرِىَ إِلَّا عَلَى ٱلَّذِى فَطَرَنِى ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿٥١﴾
وَيَٰقَوْمِ ٱسْتَغْفِرُوا۟ رَبَّكُمْ ثُمَّ تُوبُوٓا۟ إِلَيْهِ يُرْسِلِ ٱلسَّمَآءَ
عَلَيْكُم مِّدْرَارًا وَيَزِدْكُمْ قُوَّةً إِلَىٰ قُوَّتِكُمْ وَلَا تَتَوَلَّوْا
مُجْرِمِينَ ﴿٥٢﴾ قَالُوا۟ يَٰهُودُ مَا جِئْتَنَا بِبَيِّنَةٍ وَمَا نَحْنُ
بِتَارِكِىٓ ءَالِهَتِنَا عَن قَوْلِكَ وَمَا نَحْنُ لَكَ بِمُؤْمِنِينَ ﴿٥٣﴾

(46) (Allah) Ya ce: Ya Nuhu, lalle shi ba ya daga cikin iyalinka, lalle shi aiki ne marar kyau; to kada ka ƙara tambaya Ta abin da ba ka da sani a kansa; lalle Ni Ina gargaɗin ka da kada ka zamanto cikin jahilai

(47) Ya ce: "Ya Ubangijina, lalle ni ina neman tsarinka a kan in tambaye Ka abin da ba ni da sani a kansa, idan kuwa ba Ka yafe mini ba, Ka kuma ji ƙai na, to zan zamo cikin asararru."

(48) Aka ce: Ya Nuhu, ka sauka cikin aminci daga gare Mu da albarka a gare ka da kuma ga al'ummun da suke tare da kai. Wasu al'ummun kuma za Mu jiyar da su daɗi, sannan kuma azaba mai raɗaɗi daga gare Mu ta same

(49) Waɗannan suna daga labaran gaibu da muke yi maka wahayinsu, don kai da mutanenka ba ku san su ba kafin wannan (labarin); sai ka yi haƙuri; haƙiƙa kyakkyawan ƙarshe yana ga masu taƙawa

(50) Kuma (Mun aiko wa) Adawa ɗan'uwansu Hudu, ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta da gaskiya sai shi; ku ba wasu ne ba face masu ƙaga wa (Allah) ƙarya

(51) "Ya ku mutanena, ba na tambayar ku wani lada game da shi (wannan saƙo); ladana dai yana ga wanda ya ƙagi halittata. Yanzu ba za ku hankalta ba?

(52) "Kuma ya ku mutanena, ku nemi gafarar Ubangijinku sannan ku tuba gare Shi, zai sauko muku da mamakon ruwan sama, zai kuma ƙara muku ƙarfi a kan ƙarfinku, kada kuma ku ba da baya kuna masu aikata laifi."

(53) Suka ce: "Ya kai Hudu ba ka zo mana da wata hujja ba, kuma ba za mu bar abubuwan da muke bauta ba saboda maganarka, ba kuma za mu yi imani da kai ba

إِن نَّقُولُ إِلَّا ٱعۡتَرَىٰكَ بَعۡضُ ءَالِهَتِنَا بِسُوٓءٖۗ قَالَ إِنِّيٓ أُشۡهِدُ ٱللَّهَ
وَٱشۡهَدُوٓاْ أَنِّي بَرِيٓءٞ مِّمَّا تُشۡرِكُونَ ٥٤ مِن دُونِهِۦۖ فَكِيدُونِي
جَمِيعٗا ثُمَّ لَا تُنظِرُونِ ٥٥ إِنِّي تَوَكَّلۡتُ عَلَى ٱللَّهِ رَبِّي وَرَبِّكُمۚ
مَّا مِن دَآبَّةٍ إِلَّا هُوَ ءَاخِذُۢ بِنَاصِيَتِهَآۚ إِنَّ رَبِّي عَلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ
٥٦ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَقَدۡ أَبۡلَغۡتُكُم مَّآ أُرۡسِلۡتُ بِهِۦٓ إِلَيۡكُمۡۚ وَيَسۡتَخۡلِفُ
رَبِّي قَوۡمًا غَيۡرَكُمۡ وَلَا تَضُرُّونَهُۥ شَيۡـٔٗاۚ إِنَّ رَبِّي عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٍ حَفِيظٞ
٥٧ وَلَمَّا جَآءَ أَمۡرُنَا نَجَّيۡنَا هُودٗا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ بِرَحۡمَةٖ مِّنَّا
وَنَجَّيۡنَٰهُم مِّنۡ عَذَابٍ غَلِيظٖ ٥٨ وَتِلۡكَ عَادٞۖ جَحَدُواْ بِـَٔايَٰتِ
رَبِّهِمۡ وَعَصَوۡاْ رُسُلَهُۥ وَٱتَّبَعُوٓاْ أَمۡرَ كُلِّ جَبَّارٍ عَنِيدٖ ٥٩ وَأُتۡبِعُواْ فِي
هَٰذِهِ ٱلدُّنۡيَا لَعۡنَةٗ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ أَلَآ إِنَّ عَادٗا كَفَرُواْ رَبَّهُمۡۗ أَلَا
بُعۡدٗا لِّعَادٖ قَوۡمِ هُودٖ ٦٠ ۞ وَإِلَىٰ ثَمُودَ أَخَاهُمۡ صَٰلِحٗاۚ قَالَ يَٰقَوۡمِ
ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرُهُۥۖ هُوَ أَنشَأَكُم مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ
وَٱسۡتَعۡمَرَكُمۡ فِيهَا فَٱسۡتَغۡفِرُوهُ ثُمَّ تُوبُوٓاْ إِلَيۡهِۚ إِنَّ رَبِّي قَرِيبٞ مُّجِيبٞ
٦١ قَالُواْ يَٰصَٰلِحُ قَدۡ كُنتَ فِينَا مَرۡجُوّٗا قَبۡلَ هَٰذَآۖ أَتَنۡهَىٰنَآ أَن نَّعۡبُدَ
مَا يَعۡبُدُ ءَابَآؤُنَا وَإِنَّنَا لَفِي شَكّٖ مِّمَّا تَدۡعُونَآ إِلَيۡهِ مُرِيبٖ ٦٢

(54) “Ba abin da za mu faɗa sai dai kawai (mu ce) wasu abubuwan bautarmu ne suka sa maka taɓuwa.” Ya ce: “Ni lalle ina shaidar da Allah, ku ma kuma ku shaida cewa ni lalle ba ruwana da abin da kuke haɗa (Allah) da shi

(55) “Wanda ba Shi (Allah) ba; to sai ku shirya min makirci gaba ɗayanku, kar kuma ku saurara mini

(56) “Lalle ni na dogara ga Allah, Ubangijina kuma Ubangijinku. Babu wata dabba face Shi ne Yake riƙe da makwarkwaɗarta. Lalle Ubangijina a kan tafarki madaidaici Yake

(57) “To idan kuka ba da baya, haƙiƙa na isar muku abin da aka aiko ni da shi zuwa gare ku. Kuma Ubangijina zai iya musanya wasu mutanen ba ku ba, kuma ba za ku cutar da Shi da komai ba. Lalle Ubangijina Mai kula da komai ne.”

(58) Lokacin kuwa da umarninmu ya zo sai Muka tserar da Hudu shi da waɗanda suka ba da gaskiya da shi, saboda wata rahama daga gare mu, Muka kuma tserar da su daga azaba mai gwaɓi

(59) Waɗancan kuwa su ne Adawa, da suka musanta ayoyin Ubangijinsu, suka kuma saɓa wa manzanninsa, kuma suka bi umarnin duk wani mai girman kai taƙadari

(60) Aka kuma biyar musu da la’ana a duniya, haka kuma a ranar alƙiyama. Ku saurara! Lalle Adawa kam sun kafirce wa Ubangijinsu. Ku saurara! Halaka ta tabbata ga Adawa mutanen Hudu

(61) Haka kuma Muka aiko wa Samudawa ɗan’uwansu Salihu. Ya ce: “Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta ba shi ba; Shi ne Ya halicce ku daga ƙasa, Ya kuma ba ku damar ku raya ta; to ku nemi gafararsa sannan ku tuba gare Shi. Lalle Ubangijina Makusanci ne, Mai amsawa.”

(62) Suka ce: “Ya Salihu, haƙiƙa a da ka kasance a cikinmu abin yi wa (kyakkyawan) fata kafin (ka zo mana da) wannan; yanzu ka riƙa hana mu mu bauta wa abin da iyayenmu suke bauta wa? Lalle mu kam tabbas muna matuƙar shakka game da abin da kake kiran mu gare shi.”

قَالَ يَٰقَوۡمِ أَرَءَيۡتُمۡ إِن كُنتُ عَلَىٰ بَيِّنَةٖ مِّن رَّبِّي وَءَاتَىٰنِي
مِنۡهُ رَحۡمَةٗ فَمَن يَنصُرُنِي مِنَ ٱللَّهِ إِنۡ عَصَيۡتُهُۥۖ فَمَا تَزِيدُونَنِي
غَيۡرَ تَخۡسِيرٖ ٦٣ وَيَٰقَوۡمِ هَٰذِهِۦ نَاقَةُ ٱللَّهِ لَكُمۡ ءَايَةٗۖ
فَذَرُوهَا تَأۡكُلۡ فِيٓ أَرۡضِ ٱللَّهِ وَلَا تَمَسُّوهَا بِسُوٓءٖ فَيَأۡخُذَكُمۡ
عَذَابٞ قَرِيبٞ ٦٤ فَعَقَرُوهَا فَقَالَ تَمَتَّعُواْ فِي دَارِكُمۡ
ثَلَٰثَةَ أَيَّامٖۖ ذَٰلِكَ وَعۡدٌ غَيۡرُ مَكۡذُوبٖ ٦٥ فَلَمَّا جَآءَ أَمۡرُنَا
نَجَّيۡنَا صَٰلِحٗا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ بِرَحۡمَةٖ مِّنَّا وَمِنۡ
خِزۡيِ يَوۡمِئِذٍۚ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ ٱلۡقَوِيُّ ٱلۡعَزِيزُ ٦٦ وَأَخَذَ ٱلَّذِينَ
ظَلَمُواْ ٱلصَّيۡحَةُ فَأَصۡبَحُواْ فِي دِيَٰرِهِمۡ جَٰثِمِينَ ٦٧
كَأَن لَّمۡ يَغۡنَوۡاْ فِيهَآۗ أَلَآ إِنَّ ثَمُودَاْ كَفَرُواْ رَبَّهُمۡۗ أَلَا
بُعۡدٗا لِّثَمُودَ ٦٨ وَلَقَدۡ جَآءَتۡ رُسُلُنَآ إِبۡرَٰهِيمَ بِٱلۡبُشۡرَىٰ قَالُواْ
سَلَٰمٗاۖ قَالَ سَلَٰمٞۖ فَمَا لَبِثَ أَن جَآءَ بِعِجۡلٖ حَنِيذٖ ٦٩ فَلَمَّا رَءَآ
أَيۡدِيَهُمۡ لَا تَصِلُ إِلَيۡهِ نَكِرَهُمۡ وَأَوۡجَسَ مِنۡهُمۡ خِيفَةٗۚ
قَالُواْ لَا تَخَفۡ إِنَّآ أُرۡسِلۡنَآ إِلَىٰ قَوۡمِ لُوطٖ ٧٠ وَٱمۡرَأَتُهُۥ قَآئِمَةٞ
فَضَحِكَتۡ فَبَشَّرۡنَٰهَا بِإِسۡحَٰقَ وَمِن وَرَآءِ إِسۡحَٰقَ يَعۡقُوبَ ٧١

(63) Ya ce: “Ya ku mutanena, ku ba ni labari, yanzu idan na kasance a kan bayyananniyar hujja daga Ubangijina, Ya kuma ba ni rahama (ta annabci) to wa zai kare ni daga (azabar) Allah idan na saba masa? Don haka babu abin da za ku ƙare ni da shi in ban da tabewa.”

(64) “Kuma ya ku mutanena, wannan fa taguwar Allah ce a gare ku, sai ku bar ta ta ci a ƙasar Allah, kada ku cutar da ita, sai azaba ta kusa-kusa ta afka muku.”

(65) Amma sai suka soke ta, sai ya ce (da su): “Ku ji daɗi cikin gidajenku kwana uku (rak). Wannan alƙawari ne ba abin ƙaryatawa ba.”

(66) To lokacin da umarninmu ya zo sai Muka tserar da Salihu shi da waɗanda suka yi imani tare da shi saboda wata rahama daga gare mu, kuma (Muka tserar da su) daga kunyatar wannan rana. Lalle Ubangijinka Shi ne Mai ƙarfi Mabuwayi

(67) Kuma tsawa ta kama waɗanda suka yi zalunci, sai suka wayi gari cikin gidajensu a duddurƙushe (babu rai) (68) Kamar daɗai ba su taɓa zama a cikinsu ba (gidajen). Ku saurara! Lalle Samudawa kam sun kafirce wa Ubangijinsu. Ku saurara! Halaka ta tabbata ga Samudawa

(69) Haƙiƙa kuma mazanninmu sun zo wa Ibrahimu da albishir, suka ce: “Aminci (a gare ku)”, ya ce: “Aminci (a gare ku kuma).” To bai zauna ba sai da ya kawo musu soyayyen ɗan maraƙi

(70) To lokacin da ya ga hannayensu ba sa isa gare shi (soyayyen ɗan maraƙin), sai ya shiga yin ɗari-ɗari da su(1), kuma ya ɓoye jin tsoronsu a zuciyarsa, suka ce: “Kar ka tsorata; mu an aiko mu ne zuwa ga mutanen Luɗu.”

(71) Na mkewe alikuwa kasimama, na akacheka. Basi tukambashiria (kuzaliwa mtoto) Is-haƙ, na baada ya Is-haƙ Yakubu

(1) Idan baƙo ya ci abincin da aka kawo masa wannan yakan sanya nutsuwa a zukatan masu gida da yarda da shi.

قَالَتْ يَٰوَيْلَتَىٰٓ ءَأَلِدُ وَأَنَا۠ عَجُوزٌ وَهَٰذَا بَعْلِى شَيْخًا ۖ إِنَّ هَٰذَا
لَشَىْءٌ عَجِيبٌ ﴿٧٢﴾ قَالُوٓا۟ أَتَعْجَبِينَ مِنْ أَمْرِ ٱللَّهِ ۖ رَحْمَتُ ٱللَّهِ
وَبَرَكَٰتُهُۥ عَلَيْكُمْ أَهْلَ ٱلْبَيْتِ ۚ إِنَّهُۥ حَمِيدٌ مَّجِيدٌ ﴿٧٣﴾ فَلَمَّا ذَهَبَ
عَنْ إِبْرَٰهِيمَ ٱلرَّوْعُ وَجَآءَتْهُ ٱلْبُشْرَىٰ يُجَٰدِلُنَا فِى قَوْمِ لُوطٍ ﴿٧٤﴾
إِنَّ إِبْرَٰهِيمَ لَحَلِيمٌ أَوَّٰهٌ مُّنِيبٌ ﴿٧٥﴾ يَٰٓإِبْرَٰهِيمُ أَعْرِضْ عَنْ هَٰذَآ ۖ إِنَّهُۥ
قَدْ جَآءَ أَمْرُ رَبِّكَ ۖ وَإِنَّهُمْ ءَاتِيهِمْ عَذَابٌ غَيْرُ مَرْدُودٍ ﴿٧٦﴾ وَلَمَّا
جَآءَتْ رُسُلُنَا لُوطًا سِىٓءَ بِهِمْ وَضَاقَ بِهِمْ ذَرْعًا وَقَالَ هَٰذَا
يَوْمٌ عَصِيبٌ ﴿٧٧﴾ وَجَآءَهُۥ قَوْمُهُۥ يُهْرَعُونَ إِلَيْهِ وَمِن قَبْلُ كَانُوا۟
يَعْمَلُونَ ٱلسَّيِّـَٔاتِ ۚ قَالَ يَٰقَوْمِ هَٰٓؤُلَآءِ بَنَاتِى هُنَّ أَطْهَرُ لَكُمْ ۖ
فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَلَا تُخْزُونِ فِى ضَيْفِى ۖ أَلَيْسَ مِنكُمْ رَجُلٌ رَّشِيدٌ ﴿٧٨﴾
قَالُوا۟ لَقَدْ عَلِمْتَ مَا لَنَا فِى بَنَاتِكَ مِنْ حَقٍّ وَإِنَّكَ لَتَعْلَمُ مَا نُرِيدُ
﴿٧٩﴾ قَالَ لَوْ أَنَّ لِى بِكُمْ قُوَّةً أَوْ ءَاوِىٓ إِلَىٰ رُكْنٍ شَدِيدٍ ﴿٨٠﴾ قَالُوا۟
يَٰلُوطُ إِنَّا رُسُلُ رَبِّكَ لَن يَصِلُوٓا۟ إِلَيْكَ ۖ فَأَسْرِ بِأَهْلِكَ بِقِطْعٍ
مِّنَ ٱلَّيْلِ وَلَا يَلْتَفِتْ مِنكُمْ أَحَدٌ إِلَّا ٱمْرَأَتَكَ ۖ إِنَّهُۥ مُصِيبُهَا
مَآ أَصَابَهُمْ ۚ إِنَّ مَوْعِدَهُمُ ٱلصُّبْحُ ۚ أَلَيْسَ ٱلصُّبْحُ بِقَرِيبٍ ﴿٨١﴾

(72) Ta ce: “Kaicona! Yanzu zan iya haihuwa, ga ni tsohuwa kuma ga mijina nan ma tsoho? Lalle wannan abin mamaki ne!”

(73) Suka ce: “Yanzu kya rika mamaki game da al’amarin Allah? Rahamar Allah da albarkarsa su tabbata a gare ku mutanen wannan gidan. Lalle shi (Allah) Sha-yabo ne Mai girma.”

(74) To lokacin da tsoro ya rabu da Ibrahimu, kuma albishir ya zo masa, (sai ya zama) yana muhawara da Mu[1] game da mutanen Ludu

(75) Lalle Ibrahimu tabbas mai hakuri ne mai yawan ambato Allah mai yawan komawa gare Shi

(76) Ya kai Ibrahimu, ka kau da kai daga wannan. Lalle umarnin Ubangijinka ya zo; lalle kuwa azaba wadda ba mai kawar da ita za ta zo musu

(77) Lokacin kuma da manzanninmu suka zo wa Ludu, sai aka bata masa rai saboda su, kuma zuciyarsa ta yi kunci saboda su[2], ya kuma ce: “Wannan rana ce mawuyaciya!”

(78) Mutanensa kuwa suka zo masa suna gaggawa, da ma ko can sun zamanto suna yin munanan ayyuka[3]. Ya ce: “Ya ku mutanena, ga ‘ya’yana nan mata, su suka fi tsarkaka a gare ku (ba maza ba), to ku kiyayi Allah, kada ku kunyata ni game da bakina. Yanzu a cikinku ba wani mutum mai hankali?”

(79) Suka ce: “Hakika ka sani ba mu da wani hakki (na sha’awa) ga ‘ya’yanka mata, lalle kuma tabbas ka san abin da muke nufi!”(80)Ya ce: “Ina ma ina da karfi da zan hana ku, ko kuwa ina da wata kakkarfar majingina (da zan dogara da ita)?”

(81) (Bakin) suka ce: “Ya Ludu, lalle mu manzannin Ubangijinka ne; ba za su iya isowa gare ka ba; don haka sai ka tafi kai da iyalanka cikin wani yanki na dare, kada kuwa daya daga cikinku ya waiwaya, sai matarka kawai. Lalle ita kam abin da ya same su zai same ta. Lalle lokacin da aka debar musu asuba ne kawai; shin asuba ba kurkusa take ba?

(1) Watau yana muhawara da mala’ikun Allah.

(2) Watau ya shiga damuwa domin ya san mutanensa ba za su kyale su ba.

(3) Watau neman maza da yi musu fyade.

فَلَمَّا جَآءَ أَمۡرُنَا جَعَلۡنَا عَٰلِيَهَا سَافِلَهَا وَأَمۡطَرۡنَا عَلَيۡهَا
حِجَارَةٗ مِّن سِجِّيلٖ مَّنضُودٖ ٨٢ مُّسَوَّمَةً عِندَ رَبِّكَۖ
وَمَا هِيَ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ بِبَعِيدٖ ٨٣ ۞ وَإِلَىٰ مَدۡيَنَ أَخَاهُمۡ
شُعَيۡبٗاۚ قَالَ يَٰقَوۡمِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرُهُۥۖ
وَلَا تَنقُصُواْ ٱلۡمِكۡيَالَ وَٱلۡمِيزَانَۖ إِنِّيٓ أَرَىٰكُم بِخَيۡرٖ
وَإِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ عَذَابَ يَوۡمٖ مُّحِيطٖ ٨٤ وَيَٰقَوۡمِ
أَوۡفُواْ ٱلۡمِكۡيَالَ وَٱلۡمِيزَانَ بِٱلۡقِسۡطِۖ وَلَا تَبۡخَسُواْ ٱلنَّاسَ
أَشۡيَآءَهُمۡ وَلَا تَعۡثَوۡاْ فِي ٱلۡأَرۡضِ مُفۡسِدِينَ ٨٥ بَقِيَّتُ
ٱللَّهِ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَۚ وَمَآ أَنَا۠ عَلَيۡكُم
بِحَفِيظٖ ٨٦ قَالُواْ يَٰشُعَيۡبُ أَصَلَوٰتُكَ تَأۡمُرُكَ أَن نَّتۡرُكَ
مَا يَعۡبُدُ ءَابَآؤُنَآ أَوۡ أَن نَّفۡعَلَ فِيٓ أَمۡوَٰلِنَا مَا نَشَٰٓؤُاْۖ إِنَّكَ
لَأَنتَ ٱلۡحَلِيمُ ٱلرَّشِيدُ ٨٧ قَالَ يَٰقَوۡمِ أَرَءَيۡتُمۡ إِن كُنتُ
عَلَىٰ بَيِّنَةٖ مِّن رَّبِّي وَرَزَقَنِي مِنۡهُ رِزۡقٗا حَسَنٗاۚ وَمَآ أُرِيدُ أَنۡ
أُخَالِفَكُمۡ إِلَىٰ مَآ أَنۡهَىٰكُمۡ عَنۡهُۚ إِنۡ أُرِيدُ إِلَّا ٱلۡإِصۡلَٰحَ
مَا ٱسۡتَطَعۡتُۚ وَمَا تَوۡفِيقِيٓ إِلَّا بِٱللَّهِۚ عَلَيۡهِ تَوَكَّلۡتُ وَإِلَيۡهِ أُنِيبُ ٨٨



(82) To lokacin da umarninmu ya zo sai Muka mai da samanta ƙasa (wato alƙaryar), Muka kuma yi mata ruwan duwatsu irin na soyayyen yumɓu wasu bayan wasu

(83) Waɗanda aka yi wa alama daga Ubangijinka. Ba kuwa nesa (dutsen) yake da azzalumai ba

(84) Kuma Mun aiko wa (mutanen) Madyana ɗan'uwansu Shu'aibu, ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta ba shi ba, kada kuma ku tauye mudu da sikeli; lalle ni ina ganin ku da alheri (wato wadata), kuma lalle ni ina jiye muku tsoron azabar wata rana mai kewayewa

(85) "Kuma ya ku mutanena, ku cika mudu da sikeli da adalci; kada kuwa ku tauye wa mutane abubuwansu, kada kuma ku yaɗa ɓarna a bayan ƙasa

(86) "Abin da zai wanzu a gare ku na alheri a wurin Allah shi ya fi muku in kun kasance muminai. Ni kuma ba mai tsaron ku ba ne."

(87) Suka ce: "Ya kai Shu'aibu, yanzu sallarka ce[1] take umartar ka da (ka sa) mu bar abin da iyayenmu suke bauta wa, kada kuma mu aikata abin da muka ga dama da dukiyoyinmu? Lalle tabbas kai ne mai haƙuri mai hankali!"

(88) Ya ce: "Ya ku mutanena, me kuke gani ne, idan na kasance a kan bayyananniyar hujja daga Ubangijina, Ya kuma arzuta ni da kyakkyawan arziki daga gare Shi. Ba na kuma nufin in aikata abin da nake hana ku aikata shi. Ba komai nake nufi ba sai gyara iyakacin ikona. Kuma dacewata daga Allah kaɗai take. A gare Shi na dogara, kuma zuwa gare Shi ne zan koma

(1) Annabi Shu'aibu mutum ne mai yawan salla har ya shahara da haka a tsakanin mutanensa.

وَيَٰقَوۡمِ لَا يَجۡرِمَنَّكُمۡ شِقَاقِيٓ أَن يُصِيبَكُم مِّثۡلُ مَآ أَصَابَ
قَوۡمَ نُوحٍ أَوۡ قَوۡمَ هُودٍ أَوۡ قَوۡمَ صَٰلِحٖۚ وَمَا قَوۡمُ لُوطٖ مِّنكُم
بِبَعِيدٖ ٨٩ وَٱسۡتَغۡفِرُواْ رَبَّكُمۡ ثُمَّ تُوبُوٓاْ إِلَيۡهِۚ إِنَّ رَبِّي
رَحِيمٞ وَدُودٞ ٩٠ قَالُواْ يَٰشُعَيۡبُ مَا نَفۡقَهُ كَثِيرٗا مِّمَّا تَقُولُ
وَإِنَّا لَنَرَىٰكَ فِينَا ضَعِيفٗاۖ وَلَوۡلَا رَهۡطُكَ لَرَجَمۡنَٰكَۖ وَمَآ أَنتَ
عَلَيۡنَا بِعَزِيزٖ ٩١ قَالَ يَٰقَوۡمِ أَرَهۡطِيٓ أَعَزُّ عَلَيۡكُم مِّنَ ٱللَّهِ
وَٱتَّخَذۡتُمُوهُ وَرَآءَكُمۡ ظِهۡرِيًّاۖ إِنَّ رَبِّي بِمَا تَعۡمَلُونَ
مُحِيطٞ ٩٢ وَيَٰقَوۡمِ ٱعۡمَلُواْ عَلَىٰ مَكَانَتِكُمۡ إِنِّي عَٰمِلٞۖ
سَوۡفَ تَعۡلَمُونَ مَن يَأۡتِيهِ عَذَابٞ يُخۡزِيهِ وَمَنۡ هُوَ كَٰذِبٞۖ
وَٱرۡتَقِبُوٓاْ إِنِّي مَعَكُمۡ رَقِيبٞ ٩٣ وَلَمَّا جَآءَ أَمۡرُنَا نَجَّيۡنَا
شُعَيۡبٗا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ بِرَحۡمَةٖ مِّنَّا وَأَخَذَتِ
ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ ٱلصَّيۡحَةُ فَأَصۡبَحُواْ فِي دِيَٰرِهِمۡ جَٰثِمِينَ ٩٤
كَأَن لَّمۡ يَغۡنَوۡاْ فِيهَآۗ أَلَا بُعۡدٗا لِّمَدۡيَنَ كَمَا بَعِدَتۡ ثَمُودُ ٩٥
وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَا وَسُلۡطَٰنٖ مُّبِينٍ ٩٦ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ
وَمَلَإِيْهِ فَٱتَّبَعُوٓاْ أَمۡرَ فِرۡعَوۡنَۖ وَمَآ أَمۡرُ فِرۡعَوۡنَ بِرَشِيدٖ ٩٧

(89) “Kuma ya mutanena, kada saba mini ya jawo muku irin abin da ya sami mutanen Nuhu ko mutanen Hudu ko kuma mutanen Salihu, ku ma ya same ku. Mutanen Ludu kuwa ba nesa suke da ku ba

(90) “Kuma ku nemi gafarar Ubangijinku, sannan ku tuba gare Shi. Lalle Ubangijina Mai yawan rahama ne Mai nuna kauna.”

(91) Suka ce: “Ya kai Shu’aibu, ba ma fahimtar da yawa daga abin da kake faɗa; lalle kuma tabbas muna ganin ka rarrauna a cikinmu, kuma ba don danginka ba da mun jefe ka; ba kuwa za ka gagare mu ba.”

(92) Ya ce: “Ya ku mutanena, yanzu dangin nawa ne suka fi Allah girma a wurinku, kuka kuma ɗauke shi abin jefarwa a can bayanku? Lalle Ubangijina a kewaye Yake da (sanin) abin da kuke aikatawa

(93) “Kuma ya ku mutanena, ku yi aiki a kan irin hanyarku; ni ma lalle mai yin aiki ne (a kan tawa). Ba da daɗewa ba za ku san wanda azaba mai wulakantawa za ta zo masa, da kuma wanda yake maƙaryaci. Ku saurara, ni ma lalle mai sauraro ne tare da ku.”

(94) Lokacin kuwa da umarninmu ya zo Muka tserar da Shu’aibu tare da waɗanda suka yi imani da shi da wata rahama daga gare mu; tsawa kuma ta kama waɗanda suka kafirta, sai suka wayi gari cikin gidajensu a duddurƙushe, (ba rai)

(95) Kamar daɗai ba su taba zama ba a cikinsu (gidajen) ba. Ku saurara; halaka ta tabbata ga (mutanen) Madyana kamar yadda Samudawa suka halaka

(96) Haƙiƙa kuma Mun aiko Musa da ayoyinmu da hijjoji bayyanannu

(97) Zuwa ga Fir’auna da manyan fadawansa, sai suka bi umarnin Fir’auna; amma kuma umarnin Fir’auna ba a kan hanya yake ba

يَقْدُمُ قَوْمَهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فَأَوْرَدَهُمُ ٱلنَّارَ ۖ وَبِئْسَ ٱلْوِرْدُ
ٱلْمَوْرُودُ ﴿٩٨﴾ وَأُتْبِعُوا۟ فِى هَٰذِهِۦ لَعْنَةً وَيَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۚ بِئْسَ
ٱلرِّفْدُ ٱلْمَرْفُودُ ﴿٩٩﴾ ذَٰلِكَ مِنْ أَنۢبَآءِ ٱلْقُرَىٰ نَقُصُّهُۥ عَلَيْكَ ۖ
مِنْهَا قَآئِمٌ وَحَصِيدٌ ﴿١٠٠﴾ وَمَا ظَلَمْنَٰهُمْ وَلَٰكِن ظَلَمُوٓا۟
أَنفُسَهُمْ ۖ فَمَآ أَغْنَتْ عَنْهُمْ ءَالِهَتُهُمُ ٱلَّتِى يَدْعُونَ مِن دُونِ
ٱللَّهِ مِن شَىْءٍ لَّمَّا جَآءَ أَمْرُ رَبِّكَ ۖ وَمَا زَادُوهُمْ غَيْرَ تَتْبِيبٍ ﴿١٠١﴾
وَكَذَٰلِكَ أَخْذُ رَبِّكَ إِذَآ أَخَذَ ٱلْقُرَىٰ وَهِىَ ظَٰلِمَةٌ ۚ إِنَّ أَخْذَهُۥٓ
أَلِيمٌ شَدِيدٌ ﴿١٠٢﴾ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً لِّمَنْ خَافَ عَذَابَ ٱلْءَاخِرَةِ ۚ
ذَٰلِكَ يَوْمٌ مَّجْمُوعٌ لَّهُ ٱلنَّاسُ وَذَٰلِكَ يَوْمٌ مَّشْهُودٌ ﴿١٠٣﴾
وَمَا نُؤَخِّرُهُۥٓ إِلَّا لِأَجَلٍ مَّعْدُودٍ ﴿١٠٤﴾ يَوْمَ يَأْتِ لَا تَكَلَّمُ نَفْسٌ
إِلَّا بِإِذْنِهِۦ ۚ فَمِنْهُمْ شَقِىٌّ وَسَعِيدٌ ﴿١٠٥﴾ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ شَقُوا۟ فَفِى
ٱلنَّارِ لَهُمْ فِيهَا زَفِيرٌ وَشَهِيقٌ ﴿١٠٦﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَا مَا دَامَتِ ٱلسَّمَٰوَٰتُ
وَٱلْأَرْضُ إِلَّا مَا شَآءَ رَبُّكَ ۚ إِنَّ رَبَّكَ فَعَّالٌ لِّمَا يُرِيدُ ﴿١٠٧﴾
* وَأَمَّا ٱلَّذِينَ سُعِدُوا۟ فَفِى ٱلْجَنَّةِ خَٰلِدِينَ فِيهَا مَا دَامَتِ
ٱلسَّمَٰوَٰتُ وَٱلْأَرْضُ إِلَّا مَا شَآءَ رَبُّكَ ۖ عَطَآءً غَيْرَ مَجْذُوذٍ ﴿١٠٨﴾

(98) Zai jagoranci mutanensa ranar alkiyama sai ya shigar da su wuta. Kuma tir da shiga wannan mashiga
(99) Aka kuma bi su da la'ana a wannan (duniyar) da kuma ranar alkiyama. Irin wannan kyauta kuwa da aka yi musu ta munana
(100) Wadannan suna daga labarun alkaryu da Muke labarta maka su; daga cikinsu akwai wadanda suke tsaye da wadanda suke a rushe (101) Ba Mu kuwa zalunce su ba, sai dai su ne suka zalunci kansu; allolinsu da suke bauta wa ba Allah ba, ba su maganta musu komai ba, lokacin da umarnin Ubangijinka ya zo; ba su kuwa kara musu komai ba in ban da halaka
(102) Haka kuwa damkar Ubangijinka take idan ya damki alkaryu yayin da suka yi zalunci. Hakika damkarsa mai radadi ce mai tsanani
(103) Lalle game da wannan akwai aya ga wanda ya ji tsoron azabar lahira. Wannan kuwa rana ce da za a tattara mutane a cikinta, kuma wannan rana ce wadda kowa zai halarta
(104) Kuma ba ma jinkirta ta sai zuwa lokaci kayyadadde
(105) Ranar da za ta zo ba wani mai rai da zai yi magana sai da izininsa. To daga cikinsu akwai tabadde da kuma mai rabauta(106) To wadanda suka tabe suna cikin wuta suna ta kururuwa da ihu a cikinta (107) Suna madawwama a cikinta matukar sammai da kasa suna nan a dawwame, sai dai abin da Ubangijinka Ya ga dama. Lalle Ubangijinka Mai yawan aikata abin da Yake nufi ne
(108) Amma wadanda aka yi musu dace da rabauta, to suna cikin Aljanna suna masu dawwama a cikinta matukar sammai da kasa suna nan a dawwame, sai dai abin da Ubangijinka Ya ga dama, (wannan) kyauta ce marar yankewa

فَلَا تَكُ فِي مِرْيَةٍ مِّمَّا يَعْبُدُ هَٰٓؤُلَآءِ ۚ مَا يَعْبُدُونَ إِلَّا كَمَا يَعْبُدُ
ءَابَآؤُهُم مِّن قَبْلُ ۚ وَإِنَّا لَمُوَفُّوهُمْ نَصِيبَهُمْ غَيْرَ مَنقُوصٍ
﴿١٠٩﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ فَٱخْتُلِفَ فِيهِ ۚ وَلَوْلَا كَلِمَةٌ
سَبَقَتْ مِن رَّبِّكَ لَقُضِىَ بَيْنَهُمْ ۚ وَإِنَّهُمْ لَفِى شَكٍّ مِّنْهُ مُرِيبٍ
﴿١١٠﴾ وَإِنَّ كُلًّا لَّمَّا لَيُوَفِّيَنَّهُمْ رَبُّكَ أَعْمَٰلَهُمْ ۚ إِنَّهُۥ بِمَا يَعْمَلُونَ
خَبِيرٌ ﴿١١١﴾ فَٱسْتَقِمْ كَمَآ أُمِرْتَ وَمَن تَابَ مَعَكَ وَلَا تَطْغَوْا ۚ
إِنَّهُۥ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿١١٢﴾ وَلَا تَرْكَنُوٓا۟ إِلَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟
فَتَمَسَّكُمُ ٱلنَّارُ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِنْ أَوْلِيَآءَ ثُمَّ
لَا تُنصَرُونَ ﴿١١٣﴾ وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ طَرَفَىِ ٱلنَّهَارِ وَزُلَفًا مِّنَ
ٱلَّيْلِ ۚ إِنَّ ٱلْحَسَنَٰتِ يُذْهِبْنَ ٱلسَّيِّـَٔاتِ ۚ ذَٰلِكَ ذِكْرَىٰ
لِلذَّٰكِرِينَ ﴿١١٤﴾ وَٱصْبِرْ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجْرَ ٱلْمُحْسِنِينَ
﴿١١٥﴾ فَلَوْلَا كَانَ مِنَ ٱلْقُرُونِ مِن قَبْلِكُمْ أُو۟لُوا۟ بَقِيَّةٍ يَنْهَوْنَ
عَنِ ٱلْفَسَادِ فِى ٱلْأَرْضِ إِلَّا قَلِيلًا مِّمَّنْ أَنجَيْنَا مِنْهُمْ ۗ وَٱتَّبَعَ
ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ مَآ أُتْرِفُوا۟ فِيهِ وَكَانُوا۟ مُجْرِمِينَ ﴿١١٦﴾ وَمَا
كَانَ رَبُّكَ لِيُهْلِكَ ٱلْقُرَىٰ بِظُلْمٍ وَأَهْلُهَا مُصْلِحُونَ ﴿١١٧﴾



(109) To kada ka zamo cikin kokwanto dangane da abin da waɗannan suke bauta wa. Ba sa bauta sai kamar yadda iyayensu a da can suke bautar. Lalle kuma tabbas za Mu cika musu sakamakonsu ba da tauyewa ba

(110) Haƙiƙa kuma Mun bai wa Musa Littafi, sai aka sassaɓa a game da shi. Ba don kuwa wata kalma da ta rigaya daga Ubangijinka ba, to lalle da an yi hukunci a tsakaninsu. Kuma lalle suna cikin matuƙar kokwanto game da shi (Alƙur'ani)

(111) Kuma lalle kowannensu tabbas sai Ubangijinka Ya cika musu sakamakon ayyukansu. Lalle Shi Masanin abin da suke aikatawa ne

(112) Don haka sai ka tsaya totar kamar yadda aka umarce ka kai da waɗanda suka tuba tare da kai, kada kuwa ku wuce iyaka. Lalle Shi (Allah) Mai ganin abin da kuke aikatawa ne

(113) Kuma kada ku karkata zuwa ga waɗanda suka yi zalunci, sai wuta ta shafe ku, ba ku kuwa da wasu majiɓinta lamura ba Allah ba, sannan ba za a taimake ku ba

(114) Ka kuma tsai da salla farkon rana da ƙarshenta da kuma farkon dare. Lalle kyawawan (ayyuka) suna shafe munana. Wannan tunasarwa ne ga masu tunawa

(115) Kuma ka yi haƙuri, domin lalle Allah ba Ya tozarta ladan masu kyautatawa

(116) Ina ma da a ce an samu mutanen kirki daga tsarekun da suka gabace ku da za su riƙa hana yaɗuwar ɓarna a bayan ƙasa? Sai 'yan kaɗan kawai (aka samu) daga waɗanda Muka tserar cikinsu. Waɗanda kuma suka yi zalunci sai suka bi abin da aka wadata su da shi, suka kuwa zamanto masu laifi

(117) Kuma Ubangijinka bai kasance mai hallaka alƙarya ba da zalunci alhali kuwa mutanenta suna masu gyara


وَلَوْ شَآءَ رَبُّكَ لَجَعَلَ ٱلنَّاسَ أُمَّةً وَٰحِدَةً وَلَا يَزَالُونَ مُخْتَلِفِينَ ﴿١١٨﴾ إِلَّا مَن رَّحِمَ رَبُّكَ وَلِذَٰلِكَ خَلَقَهُمْ وَتَمَّتْ كَلِمَةُ رَبِّكَ لَأَمْلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنَ ٱلْجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ أَجْمَعِينَ ﴿١١٩﴾ وَكُلًّا نَّقُصُّ عَلَيْكَ مِنْ أَنۢبَآءِ ٱلرُّسُلِ مَا نُثَبِّتُ بِهِۦ فُؤَادَكَ وَجَآءَكَ فِى هَٰذِهِ ٱلْحَقُّ وَمَوْعِظَةٌ وَذِكْرَىٰ لِلْمُؤْمِنِينَ ﴿١٢٠﴾ وَقُل لِّلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ ٱعْمَلُوا۟ عَلَىٰ مَكَانَتِكُمْ إِنَّا عَٰمِلُونَ ﴿١٢١﴾ وَٱنتَظِرُوٓا۟ إِنَّا مُنتَظِرُونَ ﴿١٢٢﴾ وَلِلَّهِ غَيْبُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَإِلَيْهِ يُرْجَعُ ٱلْأَمْرُ كُلُّهُۥ فَٱعْبُدْهُ وَتَوَكَّلْ عَلَيْهِ وَمَا رَبُّكَ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿١٢٣﴾

سُورَةُ يُوسُفَ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓر تِلْكَ ءَايَٰتُ ٱلْكِتَٰبِ ٱلْمُبِينِ ﴿١﴾ إِنَّآ أَنزَلْنَٰهُ قُرْءَٰنًا عَرَبِيًّا لَّعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿٢﴾ نَحْنُ نَقُصُّ عَلَيْكَ أَحْسَنَ ٱلْقَصَصِ بِمَآ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانَ وَإِن كُنتَ مِن قَبْلِهِۦ لَمِنَ ٱلْغَٰفِلِينَ ﴿٣﴾ إِذْ قَالَ يُوسُفُ لِأَبِيهِ يَٰٓأَبَتِ إِنِّى رَأَيْتُ أَحَدَ عَشَرَ كَوْكَبًا وَٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ رَأَيْتُهُمْ لِى سَٰجِدِينَ ﴿٤﴾

(118) Kuma da Ubangijinka Ya ga dama da lalle Ya yi mutane al'umma ɗaya (a kan addini ɗaya). Ba kuwa za su gushe suna masu saɓawa juna ba

(119) Sai wanda Ubangijinka Ya yi wa rahama. A kan haka kuwa Ya halicce su; kuma Kalmar Ubangijinka ta tabbata (cewa): Lalle zan cika Jahannama da aljannu da mutane baki ɗaya

(120) Muna labarta maka kowanne daga labarun manzanni, abin da za Mu kwantar da zuciyarka da shi. Gaskiya kuwa ta zo maka cikin wannan (Surar) da izina da gargaɗi ga muminai

(121) Kuma ka ce da waɗanda ba sa yin imani: "Ku yi aiki a irin hanyarku, mu ma za mu yi aiki (a irin tamu)

(122) "Kuma ku saurara, haƙiƙa (mu ma) masu sauraro ne."

(123) Kuma (sanin) gaibu na sammai da na ƙasa na Allah ne, kuma gare Shi ake komar da dukkanin al'amari. To ka bauta masa kuma ka dogara gare Shi. Ubangijinka kuwa ba gafalalle ba ne ga abin da kuke aikatawa

Sura Yusuf

(1) ALIF LAM RA[1]. Waɗannan ayoyi ne na Littafi mabayyani

(2) Lalle Mu Muka saukar da shi Alƙur'ani da (harshen) Larabci don ku hankalta

(3) Mu ne Muke labarta maka (labari) mafi kyan labartawa ta hanyar yi maka wahayin wannan Alƙur'ani, ko da yake gabaninsa kana cikin marasa sanin(sa)

(4) (Ka tuna) lokacin da Yusufu ya ce da babansa[2]: "Ya babana, lalle na yi mafarkin taurari goma sha ɗaya da rana da wata[3], na gan su suna yi min sujjada."

(1) Duba Suratul Baƙara aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Babansa shi ne Annabi Ya'aƙub ( ) ɗan Annabi Ishaƙ ( ) ɗan Annabi Ibrahim ( ).

(3) Taurari goma sha ɗaya su ne 'yan'uwansa goma sha ɗaya; rana kuwa tana nufin mahaifiyarsa; wata kuwa yana nufin mahaifinsa Annabi Ya'aƙub ( ).

قَالَ يَٰبُنَيَّ لَا تَقۡصُصۡ رُءۡيَاكَ عَلَىٰٓ إِخۡوَتِكَ فَيَكِيدُواْ لَكَ كَيۡدًاۖ
إِنَّ ٱلشَّيۡطَٰنَ لِلۡإِنسَٰنِ عَدُوّٞ مُّبِينٞ ٥ وَكَذَٰلِكَ يَجۡتَبِيكَ
رَبُّكَ وَيُعَلِّمُكَ مِن تَأۡوِيلِ ٱلۡأَحَادِيثِ وَيُتِمُّ نِعۡمَتَهُۥ عَلَيۡكَ
وَعَلَىٰٓ ءَالِ يَعۡقُوبَ كَمَآ أَتَمَّهَا عَلَىٰٓ أَبَوَيۡكَ مِن قَبۡلُ إِبۡرَٰهِيمَ
وَإِسۡحَٰقَۚ إِنَّ رَبَّكَ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٦ ۞ لَّقَدۡ كَانَ فِي يُوسُفَ
وَإِخۡوَتِهِۦٓ ءَايَٰتٞ لِّلسَّآئِلِينَ ٧ إِذۡ قَالُواْ لَيُوسُفُ وَأَخُوهُ أَحَبُّ
إِلَىٰٓ أَبِينَا مِنَّا وَنَحۡنُ عُصۡبَةٌ إِنَّ أَبَانَا لَفِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٍ ٨
ٱقۡتُلُواْ يُوسُفَ أَوِ ٱطۡرَحُوهُ أَرۡضٗا يَخۡلُ لَكُمۡ وَجۡهُ أَبِيكُمۡ
وَتَكُونُواْ مِنۢ بَعۡدِهِۦ قَوۡمٗا صَٰلِحِينَ ٩ قَالَ قَآئِلٞ مِّنۡهُمۡ
لَا تَقۡتُلُواْ يُوسُفَ وَأَلۡقُوهُ فِي غَيَٰبَتِ ٱلۡجُبِّ يَلۡتَقِطۡهُ بَعۡضُ
ٱلسَّيَّارَةِ إِن كُنتُمۡ فَٰعِلِينَ ١٠ قَالُواْ يَٰٓأَبَانَا مَا لَكَ لَا تَأۡمَنَّا عَلَىٰ
يُوسُفَ وَإِنَّا لَهُۥ لَنَٰصِحُونَ ١١ أَرۡسِلۡهُ مَعَنَا غَدٗا يَرۡتَعۡ وَيَلۡعَبۡ
وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ١٢ قَالَ إِنِّي لَيَحۡزُنُنِيٓ أَن تَذۡهَبُواْ بِهِۦ وَأَخَافُ
أَن يَأۡكُلَهُ ٱلذِّئۡبُ وَأَنتُمۡ عَنۡهُ غَٰفِلُونَ ١٣ قَالُواْ لَئِنۡ
أَكَلَهُ ٱلذِّئۡبُ وَنَحۡنُ عُصۡبَةٌ إِنَّآ إِذٗا لَّخَٰسِرُونَ ١٤

(5) Ya ce: “Ya ɗana, kada ka labarta mafarkinka ga ‘yan’uwanka, sai su shirya maka makirci; lalle Shaiɗan maƙiyi ne mai bayyana ƙiyayya ga mutum
(6) “Kamar haka ne kuma Ubangijinka zai zaɓe ka Ya kuma sanar da kai wani abu daga fassarar mafarkai, Ya kuma cika ni’imarsa a gare ka da kuma ga iyalin Ya’aƙubu kamar yadda tun tuni Ya cika ta ga iyayenka Ibrahimu da Is’haƙa. Lalle Ubangijinka Masani ne Mai hikima.”
(7) Haƙiƙa akwai ayoyi ga matambaya dangane da (labarin) Yusufu shi da ‘yan’uwansa
(8) (Ka tuna) lokacin da (‘yan’uwan) suka ce: “Lalle Yusufu da ɗan’uwansa[1] babanmu ya fi son su da mu, ga mu kuwa jama’a masu yawa. Lalle babanmu yana cikin kuskure mabayyani
(9)“Ku kashe Yusufu ko kuma ku jefa shi wata ƙasa, (yin haka) zai juyo muku fuskar babanku, sai kuma ku kasance salihai bayansa[2].”
(10) Wani mai magana daga cikinsu ya ce: “Kada ku kashe Yusufu, ku jefa shi cikin duhun kururrumar rijiya, wasu ayarin matafiya za su tsince shi, in har haka za ku yi.”
(11) Suka ce: “Ya babanmu, me ya sa ne ba ka amince mana game da Yusufu, alhali kuwa lalle mu ba shakka masu kula da shi ne?
(12) “Ka tura shi gobe tare da mu ya yi kiwo, ya kuma yi wasa, lalle kuma mu tabbas za Mu kiyaye shi.”
(13) Ya ce: “Lalle tabbas tafiyarku da shi za ta baƙanta mini rai, ina kuma tsoron kyarkeci ya cinye shi ba da saninku ba.”
(14) Suka ce: “Lalle idan kyarkeci ya cinye shi ga mu kuwa muna da yawa kuma majiya ƙarfi to ashe lalle mun taɓe.”

(1) Shi ne Binyaminu, ɗan’uwansa ne shaƙiƙi.

(2) Watau su tuba su nemi yafiyar Allah ( ).

فَلَمَّا ذَهَبُوا۟ بِهِۦ وَأَجْمَعُوٓا۟ أَن يَجْعَلُوهُ فِى غَيَٰبَتِ ٱلْجُبِّ ۚ وَأَوْحَيْنَآ
إِلَيْهِ لَتُنَبِّئَنَّهُم بِأَمْرِهِمْ هَٰذَا وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿١٥﴾ وَجَآءُوٓ
أَبَاهُمْ عِشَآءً يَبْكُونَ ﴿١٦﴾ قَالُوا۟ يَٰٓأَبَانَآ إِنَّا ذَهَبْنَا نَسْتَبِقُ
وَتَرَكْنَا يُوسُفَ عِندَ مَتَٰعِنَا فَأَكَلَهُ ٱلذِّئْبُ ۖ وَمَآ أَنتَ
بِمُؤْمِنٍ لَّنَا وَلَوْ كُنَّا صَٰدِقِينَ ﴿١٧﴾ وَجَآءُو عَلَىٰ قَمِيصِهِۦ
بِدَمٍ كَذِبٍ ۚ قَالَ بَلْ سَوَّلَتْ لَكُمْ أَنفُسُكُمْ أَمْرًا ۖ فَصَبْرٌ جَمِيلٌ ۖ
وَٱللَّهُ ٱلْمُسْتَعَانُ عَلَىٰ مَا تَصِفُونَ ﴿١٨﴾ وَجَآءَتْ سَيَّارَةٌ
فَأَرْسَلُوا۟ وَارِدَهُمْ فَأَدْلَىٰ دَلْوَهُۥ ۖ قَالَ يَٰبُشْرَىٰ هَٰذَا غُلَٰمٌ ۚ وَأَسَرُّوهُ
بِضَٰعَةً ۚ وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِمَا يَعْمَلُونَ ﴿١٩﴾ وَشَرَوْهُ بِثَمَنٍۭ بَخْسٍ
دَرَٰهِمَ مَعْدُودَةٍ وَكَانُوا۟ فِيهِ مِنَ ٱلزَّٰهِدِينَ ﴿٢٠﴾ وَقَالَ
ٱلَّذِى ٱشْتَرَىٰهُ مِن مِّصْرَ لِٱمْرَأَتِهِۦٓ أَكْرِمِى مَثْوَىٰهُ عَسَىٰٓ
أَن يَنفَعَنَآ أَوْ نَتَّخِذَهُۥ وَلَدًا ۚ وَكَذَٰلِكَ مَكَّنَّا لِيُوسُفَ فِى
ٱلْأَرْضِ وَلِنُعَلِّمَهُۥ مِن تَأْوِيلِ ٱلْأَحَادِيثِ ۚ وَٱللَّهُ غَالِبٌ عَلَىٰٓ
أَمْرِهِۦ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٢١﴾ وَلَمَّا بَلَغَ أَشُدَّهُۥٓ
ءَاتَيْنَٰهُ حُكْمًا وَعِلْمًا ۚ وَكَذَٰلِكَ نَجْزِى ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٢٢﴾

(15) To lokacin da suka tafi da shi suka kuma haɗu a kan su saka shi cikin duhun kururrumar rijiya. Muka kuma yi masa wahayi (da cewa): "Wallahi (wata rana) za ka ba su labarin wannan al'amari nasu alhali su ba sa jin (haka zai faru)."

(16) Suka kuwa dawo wa babansu da lisha suna kuka

(17) Suka ce: "Ya babanmu, mun tafi muna wasan rige muka kuma bar Yusufu wurin kayanmu, sai kyarkeci ya cinye shi. Ba kuwa za ka gaskanta mu ba ko da muna da gaskiya."

(18) Suka kuma zo da jinin ƙarya a rigarsa[1]. (Babansu) ya ce: "Ba haka ba ne, zuciyarku dai ta shirya muku wani abu. Saboda haka (ba ni da wani abin yi) sai haƙuri nagari; Allah kuma Shi ne wanda ake neman taimakonsa a kan abin da kuke sifantawa."

(19) Da wasu ayarin matafiya suka zo sai suka tura mai nemo musu ruwa, sai ya zura gugansa (a rijiyar); sai ya ce: "Abin farin ciki ya same ni, wannan yaro ne;" suka kuma ɓoye shi a matsayin kayan kiri. Allah kuwa Masanin abin da suke aikatawa ne

(20) Suka kuma sayar da shi araha da 'yan dirhamai ƙirgaggu, suka zamanto kuma suna masu tsantsami game da shi

(21) Wanda ya saye shi kuma daga Masar[2] ya ce da matarsa: "Ki kyautata mazauninsa, muna fatan ya amfane mu, ko kuwa mu riƙe shi a matsayin ɗa." (Allah Ya ci gaba da cewa): Kamar haka Muka tabbatar da Yusufu a bayan ƙasa don kuma Mu sanar da shi fassarar mafarkai. Allah kuwa Mai rinjaye ne a bisa al'amarinsa, sai dai yawancin mutane ba sa ganewa

(22) Y cuando se hizo un hombre le concedimos sabiduría y conocimiento. Así es como recompensamos a ƙuienes hacen el bien.

(1) Watau suka zo da rigar Yusufu caɓa-caɓa da jini don su tabbatar da gaskiyarsu, amma sun manta dabba ba za ta cinye mutum ba ba tare da yayyaga tufafin jikinsa ba.

(2) Shi ne babban minista mai kula da tattalin arziki na ƙasar Masar, ana masa laƙabi da Azizu.

وَرَٰوَدَتْهُ ٱلَّتِى هُوَ فِى بَيْتِهَا عَن نَّفْسِهِۦ وَغَلَّقَتِ ٱلْأَبْوَٰبَ
وَقَالَتْ هَيْتَ لَكَ ۚ قَالَ مَعَاذَ ٱللَّهِ ۖ إِنَّهُۥ رَبِّىٓ أَحْسَنَ مَثْوَاىَ ۖ
إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٢٣﴾ وَلَقَدْ هَمَّتْ بِهِۦ ۖ وَهَمَّ بِهَا
لَوْلَآ أَن رَّءَا بُرْهَٰنَ رَبِّهِۦ ۚ كَذَٰلِكَ لِنَصْرِفَ عَنْهُ ٱلسُّوٓءَ
وَٱلْفَحْشَآءَ ۚ إِنَّهُۥ مِنْ عِبَادِنَا ٱلْمُخْلَصِينَ ﴿٢٤﴾ وَٱسْتَبَقَا
ٱلْبَابَ وَقَدَّتْ قَمِيصَهُۥ مِن دُبُرٍ وَأَلْفَيَا سَيِّدَهَا لَدَا ٱلْبَابِ ۚ
قَالَتْ مَا جَزَآءُ مَنْ أَرَادَ بِأَهْلِكَ سُوٓءًا إِلَّآ أَن يُسْجَنَ أَوْ عَذَابٌ
أَلِيمٌ ﴿٢٥﴾ قَالَ هِىَ رَٰوَدَتْنِى عَن نَّفْسِى ۚ وَشَهِدَ شَاهِدٌ مِّنْ
أَهْلِهَآ إِن كَانَ قَمِيصُهُۥ قُدَّ مِن قُبُلٍ فَصَدَقَتْ وَهُوَ
مِنَ ٱلْكَٰذِبِينَ ﴿٢٦﴾ وَإِن كَانَ قَمِيصُهُۥ قُدَّ مِن دُبُرٍ فَكَذَبَتْ وَهُوَ
مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿٢٧﴾ فَلَمَّا رَءَا قَمِيصَهُۥ قُدَّ مِن دُبُرٍ قَالَ إِنَّهُۥ
مِن كَيْدِكُنَّ ۖ إِنَّ كَيْدَكُنَّ عَظِيمٌ ﴿٢٨﴾ يُوسُفُ أَعْرِضْ عَنْ
هَٰذَا ۚ وَٱسْتَغْفِرِى لِذَنۢبِكِ ۖ إِنَّكِ كُنتِ مِنَ ٱلْخَاطِـِٔينَ
﴿٢٩﴾ * وَقَالَ نِسْوَةٌ فِى ٱلْمَدِينَةِ ٱمْرَأَتُ ٱلْعَزِيزِ تُرَٰوِدُ فَتَىٰهَا
عَن نَّفْسِهِۦ ۖ قَدْ شَغَفَهَا حُبًّا ۖ إِنَّا لَنَرَىٰهَا فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٣٠﴾

(23) Wadda kuma yake ɗakinta ta yi ƙokarin ya yi lalata da ita, ta kuwa kukkulle ƙofofi, ta kuma ce: “To ka zo mana!” Ya ce: “Allah Ya kiyashe ni! Lalle shi mai gidana ne, ya kyautata mazaunina. Lalle yadda al’amarin yake su azzalumai ba sa rabauta.”

(24) Lalle kuma ta yi niyyar ta rarumo shi, shi kuma ya yi niyyar karkata gare ta, ba don ya ga wata hujja ta Ubangijinsa ba. Kamar haka (Muka nuna masa hujjar) don Mu kawar da mummunan aiki da ɓarna daga gare shi. Lalle shi yana daga bayinmu zaɓaɓɓu

(25) Suka kuma yiwo rige wajen ƙofa, sai kuwa ta yaga rigarsa daga baya, kuma suka ci karo da mijinta daf da ƙofar, ta ce: “Ba wani sakamakon da ya cancanta ga wanda ya yi nufin mummunan abu da iyalinka in ban da kawai a ɗaure shi, ko kuwa a yi masa azaba mai raɗaɗi.”(26)(Annabi Yusufu) ya ce: “Ita ce ta neme ni”. Wani shaida kuwa daga danginta ya shaida (cewa): “Idan an yaga rigarsa ta gaba, to ta yi gaskiya shi kuwa yana cikin masu ƙarya

(27) “Idan kuwa an yaga rigarsa ta baya, to ta yi ƙarya shi kuwa yana daga masu gaskiya.”

(28) To yayin da (mijin nata) ya ga an yaga rigarsa ta baya ne, sai ya ce: “Lalle wannan yana daga irin makircinku; lalle makircinku kuwa yana da girma.”

(29) “Kai Yusufu, ka kau da kai daga wannan (magana). Ke kuma ki nemi gafarar laifinki, lalle ke kin zamanto daga masu laifi.”

(30) Waɗansu mata kuma a cikin garin suka ce: “Matar Azizu tana neman yaron gidanta; tsananin son sa ya rufe mata zuciya; lalle mu dai muna ganin ta a kan kuskure mabayyani.”

فَلَمَّا سَمِعَتۡ بِمَكۡرِهِنَّ أَرۡسَلَتۡ إِلَيۡهِنَّ وَأَعۡتَدَتۡ لَهُنَّ مُتَّكَـٔٗا
وَءَاتَتۡ كُلَّ وَٰحِدَةٖ مِّنۡهُنَّ سِكِّينٗا وَقَالَتِ ٱخۡرُجۡ عَلَيۡهِنَّۖ فَلَمَّا رَأَيۡنَهُۥٓ
أَكۡبَرۡنَهُۥ وَقَطَّعۡنَ أَيۡدِيَهُنَّ وَقُلۡنَ حَٰشَ لِلَّهِ مَا هَٰذَا بَشَرًا إِنۡ هَٰذَآ
إِلَّا مَلَكٞ كَرِيمٞ ٣١ قَالَتۡ فَذَٰلِكُنَّ ٱلَّذِي لُمۡتُنَّنِي فِيهِۖ وَلَقَدۡ رَٰوَدتُّهُۥ
عَن نَّفۡسِهِۦ فَٱسۡتَعۡصَمَۖ وَلَئِن لَّمۡ يَفۡعَلۡ مَآ ءَامُرُهُۥ لَيُسۡجَنَنَّ
وَلَيَكُونٗا مِّنَ ٱلصَّٰغِرِينَ ٣٢ قَالَ رَبِّ ٱلسِّجۡنُ أَحَبُّ إِلَيَّ مِمَّا يَدۡعُونَنِيٓ
إِلَيۡهِۖ وَإِلَّا تَصۡرِفۡ عَنِّي كَيۡدَهُنَّ أَصۡبُ إِلَيۡهِنَّ وَأَكُن مِّنَ ٱلۡجَٰهِلِينَ
٣٣ فَٱسۡتَجَابَ لَهُۥ رَبُّهُۥ فَصَرَفَ عَنۡهُ كَيۡدَهُنَّۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ
ٱلۡعَلِيمُ ٣٤ ثُمَّ بَدَا لَهُم مِّنۢ بَعۡدِ مَا رَأَوُاْ ٱلۡأٓيَٰتِ لَيَسۡجُنُنَّهُۥ
حَتَّىٰ حِينٖ ٣٥ وَدَخَلَ مَعَهُ ٱلسِّجۡنَ فَتَيَانِۖ قَالَ أَحَدُهُمَآ إِنِّيٓ
أَرَىٰنِيٓ أَعۡصِرُ خَمۡرٗاۖ وَقَالَ ٱلۡأٓخَرُ إِنِّيٓ أَرَىٰنِيٓ أَحۡمِلُ فَوۡقَ رَأۡسِي
خُبۡزٗا تَأۡكُلُ ٱلطَّيۡرُ مِنۡهُۖ نَبِّئۡنَا بِتَأۡوِيلِهِۦٓۖ إِنَّا نَرَىٰكَ مِنَ
ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٣٦ قَالَ لَا يَأۡتِيكُمَا طَعَامٞ تُرۡزَقَانِهِۦٓ إِلَّا نَبَّأۡتُكُمَا
بِتَأۡوِيلِهِۦ قَبۡلَ أَن يَأۡتِيَكُمَاۚ ذَٰلِكُمَا مِمَّا عَلَّمَنِي رَبِّيٓۚ إِنِّي تَرَكۡتُ
مِلَّةَ قَوۡمٖ لَّا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَهُم بِٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ كَٰفِرُونَ ٣٧

(31) Lokacin da ta ji irin tsegungumansu, sai ta aika musu (da gayyata), ta kuma tanadar musu wurin zaman cin abinci, kuma ta bai wa kowacce ɗayarsu wuƙa, ta kuma ce (da Annabi Yusufu): "Fita ka gilma ta gabansu." Lokacin da suka gan shi sai suka girmama shi suka yanyanke hannayensu, suka kuma ce: "Tsarki ya tabbata ga Allah; ai wannan ba mutum ba ne; wannan babban mala'ika ne kawai!"

(32) Ta ce: "To wannan shi ne wanda kuka zarge ni a kansa. Haƙiƙa kuma na neme shi sai ya ƙi yarda; Wallahi kuwa in bai aikata abin da na umarce shi ba, to za a sa shi kurkuku, kuma lalle zai zamanto cikin wulaƙantattu."

(33) (Annabi Yusufu) Ya ce: "Ya Ubangijina, kurkuku shi ya fi soyuwa a gare ni kan abin da suke nema na da shi. Idan kuwa ba Ka ije mini makircinsu ba, to zan karkata gare su kuma in zama cikin jahilai."

(34) To sai Ubangijinsa Ya amsa masa, sai Ya ije masa makircin nasu. Lalle Shi ne Mai ji kuma Masani(35) Sannan bayan duk sun ga ayoyin (da suke wanke Yusufu daga zargi) sai suka ga dai cewa lalle gara su ɗaure shi har zuwa wani lokaci

(36) Wasu samari su biyu kuma suka shiga kurkukun tare da shi; ɗaya daga cikinsu ya ce: "Lalle na yi mafarki ina matsar giya." Ɗayan kuma ya ce: "Lalle na yi mafarki ina ɗauke da gurasa a kaina, tsuntsaye suna caccakar ta. Ba mu labarin fassararsa; lalle muna ganin ka kana cikin mutane nagari."

(37) Ya ce: "Babu wani abinci da za a kawo muku sai na iya ba ku labarinsa tun ma kafin a kawo muku shi. Wannan yana daga abin da Ubangijina Ya sanar da ni; lalle ni na bar hanyar mutanen da ba sa ba da gaskiya da Allah, su kuma suna masu kafircewa da ranar lahira

وَٱتَّبَعْتُ مِلَّةَ ءَابَآءِىٓ إِبْرَٰهِيمَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ ۚ مَا كَانَ
لَنَآ أَن نُّشْرِكَ بِٱللَّهِ مِن شَىْءٍ ۚ ذَٰلِكَ مِن فَضْلِ ٱللَّهِ عَلَيْنَا وَعَلَى
ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَشْكُرُونَ ﴿٣٨﴾ يَٰصَٰحِبَىِ
ٱلسِّجْنِ ءَأَرْبَابٌ مُّتَفَرِّقُونَ خَيْرٌ أَمِ ٱللَّهُ ٱلْوَٰحِدُ ٱلْقَهَّارُ
﴿٣٩﴾ مَا تَعْبُدُونَ مِن دُونِهِۦٓ إِلَّآ أَسْمَآءً سَمَّيْتُمُوهَآ أَنتُمْ
وَءَابَآؤُكُم مَّآ أَنزَلَ ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلْطَٰنٍ ۚ إِنِ ٱلْحُكْمُ إِلَّا لِلَّهِ
أَمَرَ أَلَّا تَعْبُدُوٓا۟ إِلَّآ إِيَّاهُ ۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلْقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ
ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٤٠﴾ يَٰصَٰحِبَىِ ٱلسِّجْنِ أَمَّآ أَحَدُكُمَا
فَيَسْقِى رَبَّهُۥ خَمْرًا ۖ وَأَمَّا ٱلْءَاخَرُ فَيُصْلَبُ فَتَأْكُلُ ٱلطَّيْرُ
مِن رَّأْسِهِۦ ۖ قُضِىَ ٱلْأَمْرُ ٱلَّذِى فِيهِ تَسْتَفْتِيَانِ ﴿٤١﴾ وَقَالَ
لِلَّذِى ظَنَّ أَنَّهُۥ نَاجٍ مِّنْهُمَا ٱذْكُرْنِى عِندَ رَبِّكَ فَأَنسَىٰهُ
ٱلشَّيْطَٰنُ ذِكْرَ رَبِّهِۦ فَلَبِثَ فِى ٱلسِّجْنِ بِضْعَ سِنِينَ
﴿٤٢﴾ وَقَالَ ٱلْمَلِكُ إِنِّىٓ أَرَىٰ سَبْعَ بَقَرَٰتٍ سِمَانٍ يَأْكُلُهُنَّ
سَبْعٌ عِجَافٌ وَسَبْعَ سُنۢبُلَٰتٍ خُضْرٍ وَأُخَرَ يَابِسَٰتٍ ۖ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلْمَلَأُ أَفْتُونِى فِى رُءْيَٰىَ إِن كُنتُمْ لِلرُّءْيَا تَعْبُرُونَ ﴿٤٣﴾

(38) “Na kuma bi hanyar iyayena Ibrahimu da Is’haka da kuma Yakubu. Bai kamace mu ba a ce mu tara wani abu da Allah. Wannan yana daga falalar Allah a gare mu da kuma sauran mutane, sai dai kuma yawancin mutane ba sa godewa

(39) “Ya abokaina na kurkuku, yanzu iyayen giji barkatai su suka fi, ko kuwa Allah Daya Mai rinjaye?

(40) “Ba komai kuke bauta wa ba- bayan Allah- sai wasu sunaye da kuka ƙaga ku da iyayenku, waɗanda Allah bai saukar da wata hujja game da su ba. Hukunci na Allah ne kawai; Ya yi umarni cewa kada ku bauta wa kowa sai Shi kaɗai. Wannan shi ne addini mikaƙƙe, sai dai yawancin mutane ba sa sanin (haka)


(41) “Ya abokaina na kurkuku, amma ɗaya daga cikinku zai rika shayar da mai gidansa giya ne; amma ɗaya kuwa za a tsire shi ne, sannan tsuntsaye su zo su rika cakar kansa. An zartar da al’amarin da kuke fatawa game da shi.”

(42) Kuma ya ce wa wanda ya tabbatar da cewa shi zai tsira daga cikinsu: “Ka tuna wa mai gidanka ni;” sai Shaiɗan ya mantar da shi tuna wa mai gidan nasa, sai ya zauna a kurkuku ‘yan shekaru

(43) Sarki kuma ya ce (da jama’arsa): “Lalle na yi mafarkin shanu guda bakwai masu ƙiba da wasu bakwan ƙanjamammu suna cinye su da kuma zangarnu guda bakwai koraye da wasu bakwai busassu. Ya ku manyan malamai, ku sanar da ni fassarar mafarkin nan nawa in kun iya fassara mafarki.”

قَالُوٓاْ أَضۡغَٰثُ أَحۡلَٰمٖۖ وَمَا نَحۡنُ بِتَأۡوِيلِ ٱلۡأَحۡلَٰمِ بِعَٰلِمِينَ ٤٤
وَقَالَ ٱلَّذِي نَجَا مِنۡهُمَا وَٱدَّكَرَ بَعۡدَ أُمَّةٍ أَنَا۠ أُنَبِّئُكُم بِتَأۡوِيلِهِۦ
فَأَرۡسِلُونِ ٤٥ يُوسُفُ أَيُّهَا ٱلصِّدِّيقُ أَفۡتِنَا فِي سَبۡعِ بَقَرَٰتٖ
سِمَانٖ يَأۡكُلُهُنَّ سَبۡعٌ عِجَافٞ وَسَبۡعِ سُنۢبُلَٰتٍ خُضۡرٖ
وَأُخَرَ يَابِسَٰتٖ لَّعَلِّيٓ أَرۡجِعُ إِلَى ٱلنَّاسِ لَعَلَّهُمۡ يَعۡلَمُونَ ٤٦ قَالَ
تَزۡرَعُونَ سَبۡعَ سِنِينَ دَأَبٗا فَمَا حَصَدتُّمۡ فَذَرُوهُ فِي سُنۢبُلِهِۦٓ إِلَّا
قَلِيلٗا مِّمَّا تَأۡكُلُونَ ٤٧ ثُمَّ يَأۡتِي مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ سَبۡعٞ شِدَادٞ يَأۡكُلۡنَ
مَا قَدَّمۡتُمۡ لَهُنَّ إِلَّا قَلِيلٗا مِّمَّا تُحۡصِنُونَ ٤٨ ثُمَّ يَأۡتِي مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ
عَامٞ فِيهِ يُغَاثُ ٱلنَّاسُ وَفِيهِ يَعۡصِرُونَ ٤٩ وَقَالَ ٱلۡمَلِكُ ٱئۡتُونِي
بِهِۦۖ فَلَمَّا جَآءَهُ ٱلرَّسُولُ قَالَ ٱرۡجِعۡ إِلَىٰ رَبِّكَ فَسۡـَٔلۡهُ مَا بَالُ
ٱلنِّسۡوَةِ ٱلَّٰتِي قَطَّعۡنَ أَيۡدِيَهُنَّۚ إِنَّ رَبِّي بِكَيۡدِهِنَّ عَلِيمٞ ٥٠
قَالَ مَا خَطۡبُكُنَّ إِذۡ رَٰوَدتُّنَّ يُوسُفَ عَن نَّفۡسِهِۦۚ قُلۡنَ حَٰشَ
لِلَّهِ مَا عَلِمۡنَا عَلَيۡهِ مِن سُوٓءٖۚ قَالَتِ ٱمۡرَأَتُ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡـَٰٔنَ حَصۡحَصَ
ٱلۡحَقُّ أَنَا۠ رَٰوَدتُّهُۥ عَن نَّفۡسِهِۦ وَإِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٥١ ذَٰلِكَ
لِيَعۡلَمَ أَنِّي لَمۡ أَخُنۡهُ بِٱلۡغَيۡبِ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي كَيۡدَ ٱلۡخَآئِنِينَ ٥٢

(44) Suka ce: “Ai (wannan) kwashe-kwashen mafarki ne (kawai); mu kuma ba masana fassarar mafarki ne ba.”
(45) Wanda kuwa ya tsiran nan daga cikinsu, ya kuma tuna bayan zamani mai tsawo, ya ce: “Ni zan ba ku labarin fassararsa; to ku aike ni.”
(46) (Ya zo kurkuku ya ce): “Ya Yusufu, ya mai rikon gaskiya, ka ba mu fatawar (mafarki) game da shanu bakwai masu kiba ga wasu bakwan kanjamammu suna cinye su, da kuma zangarnu guda bakwai korayr da wasu bakwai busassu, don in koma wajen mutanen (da suka turo ni) saboda su sani.”
(47) (Annabi Yusufu) ya ce: “Za ku yi noma shekara bakwai a jere; to abin da kuka girba sai ku bar shi a zangarniyarsa, sai kadan daga abin da za ku ci
(48) “Sannan bayan wannan wasu (shekarun) bakwai masu tsanani za su zo su cinye abin da kuka tanada a cikinsu, sai dan kadan daga abin da kuke adanawa
(49) “Sannan kuma wata shekara za ta zo wadda a cikinta ne mutane za su sami ruwa, a cikinta ne kuma za su tatsi (abubuwan sha).”
(50) Sarki kuwa ya ce: “Ku zo min da shi.” Lokacin da dan aiken ya zo masa (ya ce Sarki na kira), sai ya ce: “Koma wurin mai gidanka ka tambaye shi, mene ne halin matan da suka yanyanke hannayensu? Lalle Ubangijina Yana sane da makircinsu.”
(51) (Sarki) ya ce: “Mene ne labarinku lokacin da kuka nemi Yusufu da lalata?” Suka ce: “Tsarki ya tabbata ga Allah; ba mu san wani mummunan abu game da shi ba.” Matar Azizu ta ce: “Yanzu kam gaskiya ta bayyana; ni ce da kaina na nemi lalata da shi; lalle kuma shi yana cikin masu gaskiya
(52) “Wannan kuwa don ya san cewa ni ban ha’ince shi a bayan idonsa ba, kuma lalle Allah ba Ya shiryar da makircin masu ha’inci


*وَمَآ أُبَرِّئُ نَفۡسِيٓۚ إِنَّ ٱلنَّفۡسَ لَأَمَّارَةُۢ بِٱلسُّوٓءِ إِلَّا مَا رَحِمَ رَبِّيٓۚ
إِنَّ رَبِّي غَفُورٞ رَّحِيمٞ ﴿٥٣﴾ وَقَالَ ٱلۡمَلِكُ ٱئۡتُونِي بِهِۦٓ أَسۡتَخۡلِصۡهُ
لِنَفۡسِيۖ فَلَمَّا كَلَّمَهُۥ قَالَ إِنَّكَ ٱلۡيَوۡمَ لَدَيۡنَا مَكِينٌ أَمِينٞ ﴿٥٤﴾
قَالَ ٱجۡعَلۡنِي عَلَىٰ خَزَآئِنِ ٱلۡأَرۡضِۖ إِنِّي حَفِيظٌ عَلِيمٞ ﴿٥٥﴾ وَكَذَٰلِكَ
مَكَّنَّا لِيُوسُفَ فِي ٱلۡأَرۡضِ يَتَبَوَّأُ مِنۡهَا حَيۡثُ يَشَآءُۚ نُصِيبُ
بِرَحۡمَتِنَا مَن نَّشَآءُۖ وَلَا نُضِيعُ أَجۡرَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ﴿٥٦﴾ وَلَأَجۡرُ
ٱلۡأٓخِرَةِ خَيۡرٞ لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَكَانُواْ يَتَّقُونَ ﴿٥٧﴾ وَجَآءَ
إِخۡوَةُ يُوسُفَ فَدَخَلُواْ عَلَيۡهِ فَعَرَفَهُمۡ وَهُمۡ لَهُۥ مُنكِرُونَ
﴿٥٨﴾ وَلَمَّا جَهَّزَهُم بِجَهَازِهِمۡ قَالَ ٱئۡتُونِي بِأَخٖ لَّكُم مِّنۡ أَبِيكُمۡۚ أَلَا
تَرَوۡنَ أَنِّيٓ أُوفِي ٱلۡكَيۡلَ وَأَنَا۠ خَيۡرُ ٱلۡمُنزِلِينَ ﴿٥٩﴾ فَإِن لَّمۡ تَأۡتُونِي
بِهِۦ فَلَا كَيۡلَ لَكُمۡ عِندِي وَلَا تَقۡرَبُونِ ﴿٦٠﴾ قَالُواْ سَنُرَٰوِدُ عَنۡهُ أَبَاهُ
وَإِنَّا لَفَٰعِلُونَ ﴿٦١﴾ وَقَالَ لِفِتۡيَٰنِهِ ٱجۡعَلُواْ بِضَٰعَتَهُمۡ فِي رِحَالِهِمۡ
لَعَلَّهُمۡ يَعۡرِفُونَهَآ إِذَا ٱنقَلَبُوٓاْ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِمۡ لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ
﴿٦٢﴾ فَلَمَّا رَجَعُوٓاْ إِلَىٰٓ أَبِيهِمۡ قَالُواْ يَٰٓأَبَانَا مُنِعَ مِنَّا ٱلۡكَيۡلُ
فَأَرۡسِلۡ مَعَنَآ أَخَانَا نَكۡتَلۡ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ﴿٦٣﴾

(53) “Ba kuma wai ina wanke kaina ba ne. Babu shakka ɗabi’ar rai ce ta umarci mutum da yin mummunan abu, sai fa wanda Ubangijina Ya yi wa jin ƙai. Lalle Ubangijina Mai gafara ne Mai jin ƙai.”

(54) Sarki kuma ya ce: “Ku zo min da shi in mai da shi ɗan-gaban-goshina.” Lokacin da ya yi magana da shi sai ya ce: “Lalle kai kam a yau kana da matsayi (babba, kuma kai) amintacce ne a wurinmu!”

(55) (Yusufu) Ya ce: “Ka naɗa ni mai kula da taskokin ƙasa, lalle ni mai kiyaye (amana) ne, masani.”

(56) Kamar haka ne Muka kafa Yusufu a bayan ƙasa; yana zama a cikinta inda ya ga dama. Muna bayar da rahamarmu ga wanda Muka ga dama, ba kuwa za Mu tozarta ladan masu kyautatawa ba

(57) Kuma lalle ladan lahira shi ya fi ga waɗanda suka yi imani kuma suka zamanto suna kiyaye dokokin (Allah)

(58) ‘Yan’uwan Yusufu kuma suka zo suka shiga wurinsa sai ya gane su, sai dai su ba su shaida shi ba[1]

(59) Lokacin da ya haɗa musu kayan abincinsu, sai ya ce: “Ku zo min da ɗan’uwanku na wajen uba[2]. Ashe ba kwa ganin irin yadda nake cika mudu, kuma ni ne mafi kyautata wa baƙi?

(60) “To idan ba ku zo min da shi ba to fa ba ku da wani awo ke nan a wurina (nan gaba), kuma kada ma ku kusanto ni!”

(61) Suka ce: “To za mu rarrashi babansa game da shi, kuma lalle tabbas za mu aikata (haka).”

(62) (Yusufu) Ya ce da yaransa: “Ku sanya hajarsu[3]cikin jakunkunansu don su gan ta lokacin da suka koma ga iyalinsu waƙila za su dawo.”

(63) Lokacin da suka dawo wurin babansu sai suka ce: “Ya babanmu, an hana mu yin awo (nan gaba), sai ka aika mu tare da ɗan’uwanmu mu yiwo awo, lalle kuma mu tabbas za mu kula da shi.”

(1) Saboda kamanninsa sun canza bayan shekaru da ya kwashe ba ya tare da su.

(2) Shi ne shaƙiƙinsa Binyaminu.

(3) Watau kayansu da suka zo da shi domin furfure, domin idan sun gan su za su fahimci ba ciniki ya yi da su ba, wannan zai sa su dawo tare da ɗan’uwansa.

قَالَ هَلۡ ءَامَنُكُمۡ عَلَيۡهِ إِلَّا كَمَآ أَمِنتُكُمۡ عَلَىٰٓ أَخِيهِ مِن
قَبۡلُ فَٱللَّهُ خَيۡرٌ حَٰفِظٗاۖ وَهُوَ أَرۡحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ ٦٤ وَلَمَّا فَتَحُواْ
مَتَٰعَهُمۡ وَجَدُواْ بِضَٰعَتَهُمۡ رُدَّتۡ إِلَيۡهِمۡۖ قَالُواْ يَٰٓأَبَانَا
مَا نَبۡغِيۖ هَٰذِهِۦ بِضَٰعَتُنَا رُدَّتۡ إِلَيۡنَاۖ وَنَمِيرُ أَهۡلَنَا وَنَحۡفَظُ
أَخَانَا وَنَزۡدَادُ كَيۡلَ بَعِيرٖۖ ذَٰلِكَ كَيۡلٞ يَسِيرٞ ٦٥ قَالَ
لَنۡ أُرۡسِلَهُۥ مَعَكُمۡ حَتَّىٰ تُؤۡتُونِ مَوۡثِقٗا مِّنَ ٱللَّهِ لَتَأۡتُنَّنِي
بِهِۦٓ إِلَّآ أَن يُحَاطَ بِكُمۡۖ فَلَمَّآ ءَاتَوۡهُ مَوۡثِقَهُمۡ قَالَ ٱللَّهُ عَلَىٰ مَا
نَقُولُ وَكِيلٞ ٦٦ وَقَالَ يَٰبَنِيَّ لَا تَدۡخُلُواْ مِنۢ بَابٖ وَٰحِدٖ
وَٱدۡخُلُواْ مِنۡ أَبۡوَٰبٖ مُّتَفَرِّقَةٖۖ وَمَآ أُغۡنِي عَنكُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن
شَيۡءٍۖ إِنِ ٱلۡحُكۡمُ إِلَّا لِلَّهِۖ عَلَيۡهِ تَوَكَّلۡتُۖ وَعَلَيۡهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ
ٱلۡمُتَوَكِّلُونَ ٦٧ وَلَمَّا دَخَلُواْ مِنۡ حَيۡثُ أَمَرَهُمۡ أَبُوهُم مَّا كَانَ
يُغۡنِي عَنۡهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن شَيۡءٍ إِلَّا حَاجَةٗ فِي نَفۡسِ يَعۡقُوبَ
قَضَىٰهَاۚ وَإِنَّهُۥ لَذُو عِلۡمٖ لِّمَا عَلَّمۡنَٰهُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ
لَا يَعۡلَمُونَ ٦٨ وَلَمَّا دَخَلُواْ عَلَىٰ يُوسُفَ ءَاوَىٰٓ إِلَيۡهِ أَخَاهُۖ
قَالَ إِنِّيٓ أَنَا۠ أَخُوكَ فَلَا تَبۡتَئِسۡ بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٦٩

(64) Ya ce: “Yanzu anya kuwa na amince muku game da shi, ai sai dai kawai kamar yadda na amince muku game da ɗan’uwansa tun tuni; sai dai Allah ne Fiyayen Mai kiyayewa, kuma Shi ne Fiyayyen masu rahama.”
(65) Lokacin kuma da suka buɗe jakunkunansu sai suka samu hajarsu an mayar musu da ita, suka ce: “Ya babanmu, me kuma muke nema? Ai wannan hajarmu ce aka dawo mana da ita; (idan muka koma) ai za mu nemo wa iyalinmu abinci kuma mu kula da ɗan’uwanmu, kuma mu ƙara kayan raƙumi (ɗaya). Wannan (kuwa) kaya ne sassauƙa.”
(66) (Babansu) Ya ce: “Ba zan aika ku tare da shi ba, har sai kun yi min alƙawari tsakaninku da Allah lalle za ku dawo min da shi, sai dai in wata masifa ta rutsa da ku.” Lokacin da suka yi masa alƙawari sai ya ce: “Allah ne Wakili a kan abin da muke faɗa.”
(67) Ya kuma ce: “Ya ‘ya’yana, kada ku shiga (Masar) ta ƙofa guda; ku shiga ta ƙofofi daban-daban[1]. Ba zan kare muku komai daga Allah ba; ba wani hukunci sai na Allah; a gare Shi na dogara, kuma a gare Shi ne masu dogaro ya wajaba su dogara.”
(68) To lokacin da suka shiga ta inda babansu ya umarce su, (wannan) ba zai maganta musu komai ba daga Allah, sai dai wata buƙata ce a zuciyar Yakubu da ya samu biyanta. Lalle kuma shi tabbas mai ilimi ne na abin da Muka sanar da shi, sai dai yawancin mutane ba su sani ba
(69) Lokacin kuma da suka shiga wurin Yusufu sai ya janye ɗan’uwansa wajensa ya ce: “Ni fa lalle ɗan’uwanka ne; saboda haka kada ka damu da abin da suke aikatawa.”

(1) Domi kauce wa wata cutarwa da za ta iya fuskantar su, don kada ta same su gaba ɗayansu a lokaci guda.

فَلَمَّا جَهَّزَهُم بِجَهَازِهِمْ جَعَلَ ٱلسِّقَايَةَ فِي رَحْلِ أَخِيهِ
ثُمَّ أَذَّنَ مُؤَذِّنٌ أَيَّتُهَا ٱلْعِيرُ إِنَّكُمْ لَسَٰرِقُونَ ﴿٧٠﴾ قَالُوا۟
وَأَقْبَلُوا۟ عَلَيْهِم مَّاذَا تَفْقِدُونَ ﴿٧١﴾ قَالُوا۟ نَفْقِدُ صُوَاعَ ٱلْمَلِكِ
وَلِمَن جَآءَ بِهِۦ حِمْلُ بَعِيرٍ وَأَنَا۠ بِهِۦ زَعِيمٌ ﴿٧٢﴾ قَالُوا۟ تَٱللَّهِ
لَقَدْ عَلِمْتُم مَّا جِئْنَا لِنُفْسِدَ فِي ٱلْأَرْضِ وَمَا كُنَّا سَٰرِقِينَ
﴿٧٣﴾ قَالُوا۟ فَمَا جَزَٰٓؤُهُۥٓ إِن كُنتُمْ كَٰذِبِينَ ﴿٧٤﴾ قَالُوا۟ جَزَٰٓؤُهُۥ
مَن وُجِدَ فِي رَحْلِهِۦ فَهُوَ جَزَٰٓؤُهُۥ ۚ كَذَٰلِكَ نَجْزِي ٱلظَّٰلِمِينَ
﴿٧٥﴾ فَبَدَأَ بِأَوْعِيَتِهِمْ قَبْلَ وِعَآءِ أَخِيهِ ثُمَّ ٱسْتَخْرَجَهَا مِن
وِعَآءِ أَخِيهِ ۚ كَذَٰلِكَ كِدْنَا لِيُوسُفَ ۖ مَا كَانَ لِيَأْخُذَ أَخَاهُ
فِي دِينِ ٱلْمَلِكِ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ ۚ نَرْفَعُ دَرَجَٰتٍ مَّن نَّشَآءُ ۗ
وَفَوْقَ كُلِّ ذِي عِلْمٍ عَلِيمٌ ﴿٧٦﴾ ۞ قَالُوٓا۟ إِن يَسْرِقْ
فَقَدْ سَرَقَ أَخٌ لَّهُۥ مِن قَبْلُ ۚ فَأَسَرَّهَا يُوسُفُ فِي نَفْسِهِۦ
وَلَمْ يُبْدِهَا لَهُمْ ۚ قَالَ أَنتُمْ شَرٌّ مَّكَانًا ۖ وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا
تَصِفُونَ ﴿٧٧﴾ قَالُوا۟ يَٰٓأَيُّهَا ٱلْعَزِيزُ إِنَّ لَهُۥٓ أَبًا شَيْخًا كَبِيرًا
فَخُذْ أَحَدَنَا مَكَانَهُۥٓ ۖ إِنَّا نَرَىٰكَ مِنَ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٧٨﴾

(70) To lokacin da (Azizu) ya haɗa musu kayayyakinsu sai ya sanya ma'aunin a cikin kayan ɗan'uwansa, sannan mai shela ya yi yekuwa da cewa: "Ya ku waɗannan ayari, lalle ku fa tabbas ɓarayi ne!"

(71) Suka ce: (yayin da) suka juyo wajensu: "Wane abu ne ya ɓace muku?"

(72) Suka ce: "Ma'aunin Sarki ne ba mu gani ba, kuma duk wanda ya zo da shi yana da ladan kayan raƙumi guda, kuma ni ne mai lamuninsa."

(73) Suka ce: "Wallahi haƙiƙa kun sani ba mu zo don mu yi ɓarna a bayan ƙasa ba, kuma mu ba mu taɓa zama ɓarayi ba."

(74) (Mutanen Sarki) suka ce: "Mene ne horon da za a yi masa (ɓarawon) idan ƙarya kuke yi?"

(75) Suka ce: "Horonsa shi ne, wanda aka same shi a cikin kayansa, to shi ne horonsa (watau a riƙe shi)[1]. Kamar haka muke saka wa azzalumai."

(76) Sai ya fara da (binciken) jakunkunansu kafin jakar ɗan'uwansa; sannan ya fito da shi (mudun) daga jakar ɗan'uwansa. Kamar haka Muka shirya wa Yusufu; ba zai yiwu ya riƙe ɗan'uwansa ba a shari'ar Sarkin (Masar), sai dai idan Allah Ya ga dama. Muna ɗaukaka darajojin waɗanda Muka ga dama ne. Kuma duk wani mai ilimi akwai wanda yake samansa a ilimi

(77) Suka ce: "Idan har ya yi sata, to haƙiƙa ɗan'uwansa ma a da can ya taɓa yin sata." Sai Yusufu ya ɓoye wannan (maganar) a ransa bai kuma bayyana musu ita ba, yana mai cewa (a ransa): "Ku ne dai masu mummunan matsayi (a wurin Allah). Allah kuwa Shi ne Mafi sanin abin da kuke sifantawa."

(78) Suka ce: "Ya kai wannan Azizu, lalle yana da mahaifi tsoho tukuf, sai ka riƙe ɗayanmu a madadinsa; lalle kuwa muna ganin kana daga masu kyautatawa."

(1) A shari'ance duk wanda ya yi sata ana miƙa shi ga wanda ya yi wa satar ya mayar da shi bawansa.

قَالَ مَعَاذَ ٱللَّهِ أَن نَّأۡخُذَ إِلَّا مَن وَجَدۡنَا مَتَٰعَنَا عِندَهُۥٓ إِنَّآ
إِذٗا لَّظَٰلِمُونَ ٧٩ فَلَمَّا ٱسۡتَيۡـَٔسُواْ مِنۡهُ خَلَصُواْ نَجِيّٗاۖ
قَالَ كَبِيرُهُمۡ أَلَمۡ تَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ أَبَاكُمۡ قَدۡ أَخَذَ عَلَيۡكُم
مَّوۡثِقٗا مِّنَ ٱللَّهِ وَمِن قَبۡلُ مَا فَرَّطتُمۡ فِي يُوسُفَۖ فَلَنۡ أَبۡرَحَ
ٱلۡأَرۡضَ حَتَّىٰ يَأۡذَنَ لِيٓ أَبِيٓ أَوۡ يَحۡكُمَ ٱللَّهُ لِيۖ وَهُوَ خَيۡرُ ٱلۡحَٰكِمِينَ
٨٠ ٱرۡجِعُوٓاْ إِلَىٰٓ أَبِيكُمۡ فَقُولُواْ يَٰٓأَبَانَآ إِنَّ ٱبۡنَكَ سَرَقَ
وَمَا شَهِدۡنَآ إِلَّا بِمَا عَلِمۡنَا وَمَا كُنَّا لِلۡغَيۡبِ حَٰفِظِينَ
٨١ وَسۡـَٔلِ ٱلۡقَرۡيَةَ ٱلَّتِي كُنَّا فِيهَا وَٱلۡعِيرَ ٱلَّتِيٓ أَقۡبَلۡنَا فِيهَاۖ
وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَ ٨٢ قَالَ بَلۡ سَوَّلَتۡ لَكُمۡ أَنفُسُكُمۡ أَمۡرٗاۖ
فَصَبۡرٞ جَمِيلٌۖ عَسَى ٱللَّهُ أَن يَأۡتِيَنِي بِهِمۡ جَمِيعًاۚ إِنَّهُۥ هُوَ
ٱلۡعَلِيمُ ٱلۡحَكِيمُ ٨٣ وَتَوَلَّىٰ عَنۡهُمۡ وَقَالَ يَٰٓأَسَفَىٰ عَلَىٰ
يُوسُفَ وَٱبۡيَضَّتۡ عَيۡنَاهُ مِنَ ٱلۡحُزۡنِ فَهُوَ كَظِيمٞ
٨٤ قَالُواْ تَٱللَّهِ تَفۡتَؤُاْ تَذۡكُرُ يُوسُفَ حَتَّىٰ تَكُونَ حَرَضًا
أَوۡ تَكُونَ مِنَ ٱلۡهَٰلِكِينَ ٨٥ قَالَ إِنَّمَآ أَشۡكُواْ بَثِّي
وَحُزۡنِيٓ إِلَى ٱللَّهِ وَأَعۡلَمُ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٨٦

(79) Ya ce: “Allah Ya kiyaye mu da rike wani ba wanda muka sami kayanmu a wurinsa ba; idan kuwa muka yi haka to lalle mun zama azzalumai.”

(80) To lokacin da suka fitar da rai daga gare shi, sai suka kebe suna ganawa. Babbansu ya ce: “Ba ku san cewa babanku ya ɗauki alkawari daga gare ku tsakaninku da Allah ba, kuma a da can ga irin sakacin da kuka yi game da Yusufu? To ni dai ba zan bar ƙasar (Masar) ba har sai babana ya yi min izini (da komawa), ko kuwa Allah Ya hukunta (abin da Ya ga dama) da ni; Shi ne kuwa Fiyayyen masu hukunci

(81) “Sai ku koma wurin babanku ku ce da shi: “Ya babanmu, lalle ɗanka ya yi sata! Ba mu kuwa ba da shaida ba sai da abin da muka sani, ba mu kuma zamanto masu kiyaye gaibu ba[1]

(82) “Kuma ka tambayi mutanen alƙaryar da muka kasance a cikinta (watau Masar) da kuma ayarin da muka zo cikinsu. Wallahi mu kam lalle masu gaskiya ne.”

(83) Ya ce: “Ba haka ba ne, zuciyarku dai ta shirya muku wani abu. Haƙuri kawai shi ya fi kyau (gare ni). Ina sa tsammani Allah Ya kawo min su gaba ɗaya. Lalle Shi ne Masani, Mai hikima.”

(84) Sai ya kau da kai daga gare su, ya kuma ce: “Wayyo baƙin cikina game da Yusufu!” Idanuwansa kuwa suka yi fari[2]don baƙin ciki, yana cike da ɓacin rai

(85) Suka ce: “Wallahi ba za ka bar tuna Yusufu ba har sai ka tasam ma mutuwa ko sai ka zamanto cikin matattu!”

(86) Ya ce: “Ni fa kawai ina bayyana tsananin damuwata ne da baƙin cikina ga Allah, kuma ina sane da abin da ba ku sani ba game da Allah

(1) Watau ba mu san yana sata ba, domin da a ce mun sani, to ba za mu ɗaukar maka alƙawarin za mu zo maka da shi ba.

(2) Watau ya makance ya daina gani.

يَٰبَنِيَّ ٱذۡهَبُواْ فَتَحَسَّسُواْ مِن يُوسُفَ وَأَخِيهِ وَلَا تَاْيۡـَٔسُواْ
مِن رَّوۡحِ ٱللَّهِۖ إِنَّهُۥ لَا يَاْيۡـَٔسُ مِن رَّوۡحِ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلۡقَوۡمُ
ٱلۡكَٰفِرُونَ ٨٧ فَلَمَّا دَخَلُواْ عَلَيۡهِ قَالُواْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡعَزِيزُ
مَسَّنَا وَأَهۡلَنَا ٱلضُّرُّ وَجِئۡنَا بِبِضَٰعَةٖ مُّزۡجَىٰةٖ فَأَوۡفِ لَنَا
ٱلۡكَيۡلَ وَتَصَدَّقۡ عَلَيۡنَآۖ إِنَّ ٱللَّهَ يَجۡزِي ٱلۡمُتَصَدِّقِينَ
٨٨ قَالَ هَلۡ عَلِمۡتُم مَّا فَعَلۡتُم بِيُوسُفَ وَأَخِيهِ إِذۡ أَنتُمۡ
جَٰهِلُونَ ٨٩ قَالُوٓاْ أَءِنَّكَ لَأَنتَ يُوسُفُۖ قَالَ أَنَا۠ يُوسُفُ
وَهَٰذَآ أَخِيۖ قَدۡ مَنَّ ٱللَّهُ عَلَيۡنَآۖ إِنَّهُۥ مَن يَتَّقِ وَيَصۡبِرۡ فَإِنَّ
ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجۡرَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٩٠ قَالُواْ تَٱللَّهِ لَقَدۡ
ءَاثَرَكَ ٱللَّهُ عَلَيۡنَا وَإِن كُنَّا لَخَٰطِـِٔينَ ٩١ قَالَ لَا تَثۡرِيبَ
عَلَيۡكُمُ ٱلۡيَوۡمَۖ يَغۡفِرُ ٱللَّهُ لَكُمۡۖ وَهُوَ أَرۡحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ
٩٢ ٱذۡهَبُواْ بِقَمِيصِي هَٰذَا فَأَلۡقُوهُ عَلَىٰ وَجۡهِ أَبِي يَأۡتِ
بَصِيرٗا وَأۡتُونِي بِأَهۡلِكُمۡ أَجۡمَعِينَ ٩٣ وَلَمَّا فَصَلَتِ
ٱلۡعِيرُ قَالَ أَبُوهُمۡ إِنِّي لَأَجِدُ رِيحَ يُوسُفَۖ لَوۡلَآ أَن
تُفَنِّدُونِ ٩٤ قَالُواْ تَٱللَّهِ إِنَّكَ لَفِي ضَلَٰلِكَ ٱلۡقَدِيمِ ٩٥

(87) “Ya ku ‘ya’yana, ku tafi ku lalubo labarin Yusufu shi da ɗan’uwansa, kada ku ɗebe ƙauna daga rahamar Allah. Lalle ba mai ɗebe ƙauna daga rahamar Allah sai mutane kafirai.”

(88) Lokacin da suka shiga wurinsa (Annabi Yusufu) sai suka ce: “Ya Azizu, muna fama da yunwa mu da iyalanmu, kuma mun zo maka da wata haja marar daraja; to ka cika mana mudu, ka kuma kyautata mana; lalle Allah Yana saka wa masu kyautatawa.”

(89) Ya ce: “Shin kun kuwa san abin da kuka aikata wa Yusufu shi da ɗan’uwansa a lokacin da kuke jahilai?”(90)Suka ce: “Shin kuwa tabbas ko kai ne Yusufu ne?” Ya ce: “Ni ne Yusufu, wannan kuma ɗan’uwana ne; haƙiƙa Allah Ya yi mana baiwa; lalle wanda ya kiyaye dokokin (Allah) ya kuma yi haƙuri, to tabbas Allah ba Ya tozarta sakamakon masu kyautatawa.”

(91) Suka ce: “Wallahi haƙiƙa Allah Ya fifita ka a kanmu, mu kuma lalle mun tabbata masu kuskure!”

(92) Ya ce: “A yau babu wani zargi a kanku; Allah zai yafe muku, Shi ne Mafificin masu rahama

(93) “Ku tafi da rigata wannan sannan ku jefa ta a fuskar babana, zai dawo mai gani, ku kuma zo min da iyalanku gaba ɗaya.”

(94) Lokacin da ayarin ya baro (Masar) sai babansu ya ce: “Lalle ina jin ƙanshin Yusufu; ba don dai kada ku ce na susuce ba!”

(95) Suka ce: “Wallahi mun tabbata ba shakka (har yanzu) kana nan cikin ɗaɗaɗɗiyar rikicewar nan taka!”

فَلَمَّآ أَن جَآءَ ٱلْبَشِيرُ أَلْقَىٰهُ عَلَىٰ وَجْهِهِۦ فَٱرْتَدَّ بَصِيرًا ۖ قَالَ
أَلَمْ أَقُل لَّكُمْ إِنِّىٓ أَعْلَمُ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿٩٦﴾ قَالُوا۟
يَٰٓأَبَانَا ٱسْتَغْفِرْ لَنَا ذُنُوبَنَآ إِنَّا كُنَّا خَٰطِـِٔينَ ﴿٩٧﴾ قَالَ سَوْفَ
أَسْتَغْفِرُ لَكُمْ رَبِّىٓ ۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٩٨﴾ فَلَمَّا
دَخَلُوا۟ عَلَىٰ يُوسُفَ ءَاوَىٰٓ إِلَيْهِ أَبَوَيْهِ وَقَالَ ٱدْخُلُوا۟ مِصْرَ
إِن شَآءَ ٱللَّهُ ءَامِنِينَ ﴿٩٩﴾ وَرَفَعَ أَبَوَيْهِ عَلَى ٱلْعَرْشِ وَخَرُّوا۟
لَهُۥ سُجَّدًا ۖ وَقَالَ يَٰٓأَبَتِ هَٰذَا تَأْوِيلُ رُءْيَىَ مِن قَبْلُ قَدْ جَعَلَهَا
رَبِّى حَقًّا ۖ وَقَدْ أَحْسَنَ بِىٓ إِذْ أَخْرَجَنِى مِنَ ٱلسِّجْنِ وَجَآءَ بِكُم
مِّنَ ٱلْبَدْوِ مِنۢ بَعْدِ أَن نَّزَغَ ٱلشَّيْطَٰنُ بَيْنِى وَبَيْنَ إِخْوَتِىٓ ۚ إِنَّ
رَبِّى لَطِيفٌ لِّمَا يَشَآءُ ۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْحَكِيمُ ﴿١٠٠﴾ ۞ رَبِّ
قَدْ ءَاتَيْتَنِى مِنَ ٱلْمُلْكِ وَعَلَّمْتَنِى مِن تَأْوِيلِ ٱلْأَحَادِيثِ ۚ
فَاطِرَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ أَنتَ وَلِيِّۦ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ ۖ
تَوَفَّنِى مُسْلِمًا وَأَلْحِقْنِى بِٱلصَّٰلِحِينَ ﴿١٠١﴾ ذَٰلِكَ مِنْ أَنۢبَآءِ
ٱلْغَيْبِ نُوحِيهِ إِلَيْكَ ۖ وَمَا كُنتَ لَدَيْهِمْ إِذْ أَجْمَعُوٓا۟ أَمْرَهُمْ
وَهُمْ يَمْكُرُونَ ﴿١٠٢﴾ وَمَآ أَكْثَرُ ٱلنَّاسِ وَلَوْ حَرَصْتَ بِمُؤْمِنِينَ ﴿١٠٣﴾

(96) To lokacin da mai albishir ya zo masa sai ya jefa ta (rigar) a fuskarsa, sai ya dawo yana gani. Ya ce: “Ban gaya muku ba cewa lalle ni na san abin da ku ba ku sani ba game da Allah?”

(97) Suka ce: “Ya babanmu, ka nema mana gafarar zunubanmu, lalle mun zamanto masu kuskure!”

(98) Ya ce: “Ba da daɗewa ba zan nema muku gafarar Ubangijina; lalle Shi ne Mai yawan gafara, Mai jin ƙai.”

(99) Lokacin da suka shiga wurin Yusufu sai ya jawo iyayensa ya kuma ce: “Ku shigo Masar in Allah Ya ga dama kuna amintattu.”

(100) Ya kuma ɗora mahaifansa a kan gadon mulki, suka kuma faɗi suna masu gaisuwa a gare shi, ya kuma ce: “Ya babanmu, wannan shi ne fassarar mafarkina na tun tuni. Lalle Ubangijina Ya mai da shi gaskiya; haƙiƙa kuma Ya kyautata min lokacin da Ya fitar da ni daga kurkuku, Ya kuma zo da ku daga ƙauye bayan Shaiɗan ya shiga tsakanina da ‘yan’uwana. Lalle Ubangijina Mai tausasawa ne ga wanda Ya ga dama. Lalle Shi ne Masani, Mai hikima

(101) “Ya Ubangijina, haƙiƙa Ka ba ni wani abu na mulki, Ka kuma sanar da ni wani abu daga fassarar mafarki; Ya Mahaliccin sammai da ƙasa, Kai ne Majiɓincina a duniya da lahira; ka karɓi raina ina Musulmi, Ka kuma haɗa ni da (mutane) salihai.”

(102) Wannan yana daga labaran gaibu da Muke yi maka wahayinsa; ba ka kuma tare da su lokacin da suka haɗa al’amarinsu suna ƙulle-ƙullen makirci

(103) Yawancin mutane ba za su yi imani ba, komai kwaɗayinka (ga hakan)

وَمَا تَسْـَٔلُهُمْ عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ ۚ إِنْ هُوَ إِلَّا ذِكْرٌ لِّلْعَٰلَمِينَ
﴿١٠٤﴾ وَكَأَيِّن مِّنْ ءَايَةٍ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ يَمُرُّونَ عَلَيْهَا
وَهُمْ عَنْهَا مُعْرِضُونَ ﴿١٠٥﴾ وَمَا يُؤْمِنُ أَكْثَرُهُم بِٱللَّهِ إِلَّا
وَهُم مُّشْرِكُونَ ﴿١٠٦﴾ أَفَأَمِنُوٓا۟ أَن تَأْتِيَهُمْ غَٰشِيَةٌ مِّنْ عَذَابِ
ٱللَّهِ أَوْ تَأْتِيَهُمُ ٱلسَّاعَةُ بَغْتَةً وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿١٠٧﴾ قُلْ
هَٰذِهِۦ سَبِيلِىٓ أَدْعُوٓا۟ إِلَى ٱللَّهِ ۚ عَلَىٰ بَصِيرَةٍ أَنَا۠ وَمَنِ ٱتَّبَعَنِى ۖ
وَسُبْحَٰنَ ٱللَّهِ وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿١٠٨﴾ وَمَآ أَرْسَلْنَا مِن
قَبْلِكَ إِلَّا رِجَالًا نُّوحِىٓ إِلَيْهِم مِّنْ أَهْلِ ٱلْقُرَىٰ ۗ أَفَلَمْ يَسِيرُوا۟
فِى ٱلْأَرْضِ فَيَنظُرُوا۟ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن
قَبْلِهِمْ ۗ وَلَدَارُ ٱلْءَاخِرَةِ خَيْرٌ لِّلَّذِينَ ٱتَّقَوْا۟ ۗ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿١٠٩﴾
حَتَّىٰٓ إِذَا ٱسْتَيْـَٔسَ ٱلرُّسُلُ وَظَنُّوٓا۟ أَنَّهُمْ قَدْ كُذِبُوا۟
جَآءَهُمْ نَصْرُنَا فَنُجِّىَ مَن نَّشَآءُ ۖ وَلَا يُرَدُّ بَأْسُنَا عَنِ ٱلْقَوْمِ
ٱلْمُجْرِمِينَ ﴿١١٠﴾ لَقَدْ كَانَ فِى قَصَصِهِمْ عِبْرَةٌ لِّأُو۟لِى ٱلْأَلْبَٰبِ ۗ
مَا كَانَ حَدِيثًا يُفْتَرَىٰ وَلَٰكِن تَصْدِيقَ ٱلَّذِى بَيْنَ يَدَيْهِ
وَتَفْصِيلَ كُلِّ شَىْءٍ وَهُدًى وَرَحْمَةً لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿١١١﴾

(104) Kuma ba ka tambayar su lada a kansa (wato Alƙur'ani). Shi ba wani abu ne daban ba in ban da gargaɗi ga talikai

(105) Kuma ayoyi nawa ne a sammai da ƙasa waɗanda (kafirai) suke wucewa ta wajensu, amma suna bijire musu?

(106) Yawancinsu kuma ba sa yin imani da Allah sai (an same su) suna masu shirka (da Shi)

(107) Yanzu sun amince ne wata azabar Allah mai lullubewa ta zo musu, ko kuwa alƙiyama ta zo musu ba zato ba tsammani, alhalin su ba su sani ba?

(108) Ka ce: "Wannan ce hanyata, ina yin kira zuwa ga Allah, bisa hujja, ni da wanda ya bi ni. Tsarki kuma ya tabbata ga Allah, ni kuwa ba na cikin masu shirka."

(109) Ba Mu kuma aiko (manzanni) a gabaninka ba sai maza 'yan birni waɗanda Muke yi wa wahayi. Me ya sa (kafirai) ba za su yi tafiya ba a bayan ƙasa don su ga yadda ƙarshen waɗanda suka rigaye su ya kasance? Lalle kuwa gidan lahira shi ya fi ga waɗanda suke kiyaye dokokin (Allah). Shin ba za ku hankalta ba?

(110) Har yayin da manzanni suka ɗebe ƙauna (da imanin mutanensu), su kuma (kafiran) suka yi zaton an faɗa musu ƙarya ne (game da zuwan azabar Allah) sai taimakonmu ya zo musu, sai Muka tserar da wanda Muka ga dama; ba kuwa za a kawar da azabarmu daga mutane masu laifi ba

(111) Haƙiƙa akwai izina a cikin labaransu (annabawa) ga ma'abota hankali. (Alƙur'ani) bai zamanto zance ne da ake ƙirƙirar sa ba, sai dai zance ne da yake gaskata abin da ya rigaye shi (na littattafai), da kuma bayanin komai; shiriya ne kuma da rahama ga mutanen da suke yin imani

Sura Ra'ad

(

سُورَةُ الرَّعۡدِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلٓمٓرٓۚ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِۗ وَٱلَّذِيٓ أُنزِلَ إِلَيۡكَ مِن رَّبِّكَ ٱلۡحَقُّ
وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يُؤۡمِنُونَ ١ ٱللَّهُ ٱلَّذِي رَفَعَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
بِغَيۡرِ عَمَدٖ تَرَوۡنَهَاۖ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰ عَلَى ٱلۡعَرۡشِۖ وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَۖ
كُلّٞ يَجۡرِي لِأَجَلٖ مُّسَمّٗىۚ يُدَبِّرُ ٱلۡأَمۡرَ يُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ لَعَلَّكُم
بِلِقَآءِ رَبِّكُمۡ تُوقِنُونَ ٢ وَهُوَ ٱلَّذِي مَدَّ ٱلۡأَرۡضَ وَجَعَلَ فِيهَا رَوَٰسِيَ
وَأَنۡهَٰرٗاۖ وَمِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ جَعَلَ فِيهَا زَوۡجَيۡنِ ٱثۡنَيۡنِۖ يُغۡشِي ٱلَّيۡلَ
ٱلنَّهَارَۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَتَفَكَّرُونَ ٣ وَفِي ٱلۡأَرۡضِ
قِطَعٞ مُّتَجَٰوِرَٰتٞ وَجَنَّٰتٞ مِّنۡ أَعۡنَٰبٖ وَزَرۡعٞ وَنَخِيلٞ صِنۡوَانٞ
وَغَيۡرُ صِنۡوَانٖ يُسۡقَىٰ بِمَآءٖ وَٰحِدٖ وَنُفَضِّلُ بَعۡضَهَا عَلَىٰ بَعۡضٖ
فِي ٱلۡأُكُلِۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ ٤ ۞ وَإِن تَعۡجَبۡ
فَعَجَبٞ قَوۡلُهُمۡ أَءِذَا كُنَّا تُرَٰبًا أَءِنَّا لَفِي خَلۡقٖ جَدِيدٍۗ
أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِرَبِّهِمۡۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ ٱلۡأَغۡلَٰلُ فِيٓ
أَعۡنَاقِهِمۡۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٥

(1) ALIF LAM MIM RA[1] Wadannan ayoyi ne na Littafi (wato Alkur'ani). Wanda kuma aka saukar maka daga Ubangijinka gaskiya ne, sai dai lalle yawancin mutane ba sa yin imani

(2) Allah Wanda Ya daukaka sammai ba tare da wasu ginshikai da kuke ganinsu ba; sannan Ya daidaita bisa Al'arshi[2]; Ya kuma hore muku rana da wata; kowannensu yana gudu zuwa wani lokaci kayyadadde. Yana shirya al'amari, Yana bayyana ayoyi don ku sakankance da haduwarku da Ubangijinku

(3) Shi ne kuma Wanda Ya shimfida kasa Ya kuma sanya turaku (na duwatsu) a cikinta da koramu; kuma daga kowadanne 'ya'yan itace Ya sanya ma'aura biyu (mace da namiji); dare yana rufe rana. Lalle a game da wadannan abubuwan tabbas akwai ayoyi ga mutanen da suke tunani

(4) A cikin kasa kuma da akwai yankuna masu makotaka da juna, da gonakai na inabai da shuke-shuke da dabinai masu tushiya daya da kuma wadanda suke kowane tushiyarsa daban, ana shayar da su da ruwa daya[3] Muna kuma fifita wasunsu a kan wasu wajen dandano. Hakika a game da wannan da akwai ayoyi ga mutanen da suke da hankali

(5) Idan kuwa kana mamakin (karyata ka da suke yi), to ai abin mamaki shi ne fadarsu (cewa): "Yanzu idan muka zama turbaya anya kuwa za a sake halittarmu?" Wadannan su ne wadanda suka kafirce wa Ubangijinsu, wadannan kuma akwai kukumi (da za a sa musu) a wuyoyinsu. Wadannan kuwa su ne 'yan wuta madawwama a cikinta

(1) Duba Suratul Bakara, aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Duba Suratul A'araf aya ta 54, hashiya ta 126.

(3) To amma sai su fito mabambanta a kamanni da dandano da girma, duk kuwa da cewa an shuka su a kasa daya kuma s`un sha ruwa daya.

وَيَسْتَعْجِلُونَكَ بِٱلسَّيِّئَةِ قَبْلَ ٱلْحَسَنَةِ وَقَدْ خَلَتْ مِن
قَبْلِهِمُ ٱلْمَثُلَٰتُ ۗ وَإِنَّ رَبَّكَ لَذُو مَغْفِرَةٍ لِّلنَّاسِ عَلَىٰ ظُلْمِهِمْ ۖ
وَإِنَّ رَبَّكَ لَشَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿٦﴾ وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لَوْلَآ
أُنزِلَ عَلَيْهِ ءَايَةٌ مِّن رَّبِّهِۦٓ ۗ إِنَّمَآ أَنتَ مُنذِرٌ ۖ وَلِكُلِّ قَوْمٍ
هَادٍ ﴿٧﴾ ٱللَّهُ يَعْلَمُ مَا تَحْمِلُ كُلُّ أُنثَىٰ وَمَا تَغِيضُ ٱلْأَرْحَامُ
وَمَا تَزْدَادُ ۖ وَكُلُّ شَىْءٍ عِندَهُۥ بِمِقْدَارٍ ﴿٨﴾ عَٰلِمُ ٱلْغَيْبِ
وَٱلشَّهَٰدَةِ ٱلْكَبِيرُ ٱلْمُتَعَالِ ﴿٩﴾ سَوَآءٌ مِّنكُم مَّنْ
أَسَرَّ ٱلْقَوْلَ وَمَن جَهَرَ بِهِۦ وَمَنْ هُوَ مُسْتَخْفٍۭ بِٱلَّيْلِ وَسَارِبٌۢ
بِٱلنَّهَارِ ﴿١٠﴾ لَهُۥ مُعَقِّبَٰتٌ مِّنۢ بَيْنِ يَدَيْهِ وَمِنْ خَلْفِهِۦ
يَحْفَظُونَهُۥ مِنْ أَمْرِ ٱللَّهِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُغَيِّرُ مَا بِقَوْمٍ حَتَّىٰ يُغَيِّرُوا۟
مَا بِأَنفُسِهِمْ ۗ وَإِذَآ أَرَادَ ٱللَّهُ بِقَوْمٍ سُوٓءًا فَلَا مَرَدَّ لَهُۥ ۚ وَمَا
لَهُم مِّن دُونِهِۦ مِن وَالٍ ﴿١١﴾ هُوَ ٱلَّذِى يُرِيكُمُ ٱلْبَرْقَ خَوْفًا
وَطَمَعًا وَيُنشِئُ ٱلسَّحَابَ ٱلثِّقَالَ ﴿١٢﴾ وَيُسَبِّحُ ٱلرَّعْدُ بِحَمْدِهِۦ
وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ مِنْ خِيفَتِهِۦ وَيُرْسِلُ ٱلصَّوَٰعِقَ فَيُصِيبُ بِهَا
مَن يَشَآءُ وَهُمْ يُجَٰدِلُونَ فِى ٱللَّهِ وَهُوَ شَدِيدُ ٱلْمِحَالِ ﴿١٣﴾

(6) Suna kuma nemanka da gaggauto musu da azaba tun kafin (su nemi) kyakkyawa (wato rahamar Allah), alhali kuwa haƙiƙa misalai (na waɗanda aka halakar) a gabansu sun wuce. Lalle kuma Ubangijinka Ma'abocin gafara ne ga mutane a kan laifuffukansu, kuma lalle Ubangijinka tabbas Mai tsananin azaba ne

(7) Waɗanda suka kafirta suna cewa: "Me ya hana a saukar masa da wata aya daga Ubangijinsa?" Lalle kai mai gargaɗi ne kawai; kowaɗanne mutane kuwa suna da mai shiryawa

(8) Allah Yana sane da abin da (mahaifar) kowace mace take ɗauke da shi da kuma abin da mahaifa take ragewa da wanda take ƙarawa[1]; kowane abu kuma a wurinsa yana da gwargwado

(9) (Shi) Masanin abin da ke ɓoye da na sarari ne, Mai girma, Mai cikar ɗaukaka

(10) Duka ɗaya ne (a wurin Allah) wanda ya ɓoye magana daga cikinku da wanda ya bayyana ta da wanda yake ɓuya da daddare da mai bayyana da rana

(11) (Kowanensu) yana da (mala'iku) masu take masa baya a gabansa da kuma bayansa suna kiyaye shi da umarnin Allah. Lalle Allah ba Ya canja abin da mutane suke ciki har sai sun canja halayensu. Idan kuma Allah Ya yi nufin wata azaba ga mutane, to ba mai juyar da ita, ba su kuwa da wani mai jiɓintar su wanda ba Shi ba

(12)Shi ne Wanda Yake nuna muku walƙiya don tsoratarwa da kuma kwaɗaitarwa, Yake kuma haɗo hadari mai nauyi (ɗauke da ruwa)

(13) Tsawa tana tsarkake (Shi) tare da gode masa, mala'iku ma (suna tasbihi) saboda tsoron Sa, Yana kuma aiko da tsawawwaki sai Ya sami wanda Ya ga dama da su, kuma su (kafirai) ga su suna jayayya game da (sha'anin) Allah. Shi kuwa Mai tsananin ƙarfi ne

(1) Watau ana nufin lokacin haihuwarta, ko dai ta haihu kafin cikar wata tara, ko ta haihu bayan cikar wa'adin cikinta, ko ɗan ya zo cikakke da ƙoshin lafiya, ko kuma da wata nakasa ko rashin lafiya.

لَهُۥ دَعۡوَةُ ٱلۡحَقِّۖ وَٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَسۡتَجِيبُونَ لَهُم بِشَيۡءٍ إِلَّا
كَبَٰسِطِ كَفَّيۡهِ إِلَى ٱلۡمَآءِ لِيَبۡلُغَ فَاهُ وَمَا هُوَ بِبَٰلِغِهِۦۚ وَمَا دُعَآءُ ٱلۡكَٰفِرِينَ
إِلَّا فِي ضَلَٰلٖ ١٤ وَلِلَّهِ يَسۡجُدُ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ طَوۡعٗا
وَكَرۡهٗا وَظِلَٰلُهُم بِٱلۡغُدُوِّ وَٱلۡأٓصَالِ ١٥ قُلۡ مَن رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِ قُلِ ٱللَّهُۚ قُلۡ أَفَٱتَّخَذۡتُم مِّن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَ لَا يَمۡلِكُونَ
لِأَنفُسِهِمۡ نَفۡعٗا وَلَا ضَرّٗاۚ قُلۡ هَلۡ يَسۡتَوِي ٱلۡأَعۡمَىٰ وَٱلۡبَصِيرُ أَمۡ هَلۡ
تَسۡتَوِي ٱلظُّلُمَٰتُ وَٱلنُّورُۗ أَمۡ جَعَلُواْ لِلَّهِ شُرَكَآءَ خَلَقُواْ كَخَلۡقِهِۦ فَتَشَٰبَهَ
ٱلۡخَلۡقُ عَلَيۡهِمۡۚ قُلِ ٱللَّهُ خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖ وَهُوَ ٱلۡوَٰحِدُ ٱلۡقَهَّٰرُ ١٦ أَنزَلَ
مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَسَالَتۡ أَوۡدِيَةُۢ بِقَدَرِهَا فَٱحۡتَمَلَ ٱلسَّيۡلُ زَبَدٗا رَّابِيٗاۖ
وَمِمَّا يُوقِدُونَ عَلَيۡهِ فِي ٱلنَّارِ ٱبۡتِغَآءَ حِلۡيَةٍ أَوۡ مَتَٰعٖ زَبَدٞ مِّثۡلُهُۥۚ
كَذَٰلِكَ يَضۡرِبُ ٱللَّهُ ٱلۡحَقَّ وَٱلۡبَٰطِلَۚ فَأَمَّا ٱلزَّبَدُ فَيَذۡهَبُ جُفَآءٗۖ
وَأَمَّا مَا يَنفَعُ ٱلنَّاسَ فَيَمۡكُثُ فِي ٱلۡأَرۡضِۚ كَذَٰلِكَ يَضۡرِبُ ٱللَّهُ
ٱلۡأَمۡثَالَ ١٧ لِلَّذِينَ ٱسۡتَجَابُواْ لِرَبِّهِمُ ٱلۡحُسۡنَىٰۚ وَٱلَّذِينَ لَمۡ يَسۡتَجِيبُواْ
لَهُۥ لَوۡ أَنَّ لَهُم مَّا فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا وَمِثۡلَهُۥ مَعَهُۥ لَٱفۡتَدَوۡاْ بِهِۦٓۚ
أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ سُوٓءُ ٱلۡحِسَابِ وَمَأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمِهَادُ ١٨

(14) Gare Shi (Shi kaɗai) kira na gaske yake; waɗanda kuwa suke bauta wa wasu ba Shi ba, to ba sa amsa musu da komai illa tamkar wanda ya shimfiɗa tafukansa ga ruwa don ya isa bakinsa, ba kuwa zai isa gare shi ba(1). Addu'ar kafirai kuma ba a komai take ba illa a cikin ɓata

(15) Waɗanda kuma suke sammai da ƙasa (duka) ga Allah suke sujjada sun so ko sun ƙi, haka kuma inuwoyinsu, safe da maraice

(16) Ka ce (da su): "Wane ne Ubangijin sammai da ƙasa?" Ka ce: "Allah ne". Ka ce (da su): "Amma yaya kuka riƙi wasu iyayen giji ba Shi ba su zama majiɓinta (gare ku), ba sa mallakar wani amfani ko cuta ga kansu?" Ka ce: "Shin makaho da mai gani za su yi daidai, ko kuwa shin duhu da haske za su yi daidai? Ko sun sanya wa Allah wasu abokan tarayya ne waɗanda suka yi halitta kamar halittarsa, sai halittar ta yi musu kama da juna?" Ka ce: "Allah ne Mahaliccin komai, kuma Shi ne Makaɗaici, Mai rinjaye."

(17) Ya saukar da ruwa daga sama, sai magudanai suka kwarara daidai gwargwadon abin da za su iya ɗauka, sai (shi ruwan) mai kwarara ya ɗauko kumfa a samansa. Akwai kuma wata kumfar kamarta daga abin da kuke narkawa a wuta don samun abin ado ko kuwa (ƙera) abin jin daɗi. Kamar haka ne Allah Yake ba da misalin gaskiya da ɓarna. To amma kumfar sai ta tafi ta bi iska; amma kuma abin da zai amfani mutane sai ya zauna a ƙasa. Kamar haka ne Allah Yake ba da misali

(18) Waɗanda suka amsa (kiran) Ubangijinsu suna da kyakkyawar (makoma). Waɗanda kuwa ba su amsa ba, da a ce duk abin da ke ƙasa gaba ɗaya tare kuma da wani kwatankwacinsa duka nasu ne, to da lalle sun fanshi kansu da shi (ranar alƙiyama). Waɗannan suna da mummunan hisabi, kuma Jahannama ce makomarsu, kuma tir da wannan shimfiɗa

(1) Watau kamar mai shimfiɗa hannunsa a kan ruwa yana jiran ya taso ya shiga bakinsa yake yin aikin wofi, hakanan mai bautar wanin Allah shi ma yake yin bautar banza da wofi.

أَفَمَن يَعْلَمُ أَنَّمَآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ ٱلْحَقُّ كَمَنْ هُوَ أَعْمَىٰٓ ۚ إِنَّمَا يَتَذَكَّرُ
أُو۟لُوا۟ ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿١٩﴾ ٱلَّذِينَ يُوفُونَ بِعَهْدِ ٱللَّهِ وَلَا يَنقُضُونَ ٱلْمِيثَٰقَ
﴿٢٠﴾ وَٱلَّذِينَ يَصِلُونَ مَآ أَمَرَ ٱللَّهُ بِهِۦٓ أَن يُوصَلَ وَيَخْشَوْنَ رَبَّهُمْ
وَيَخَافُونَ سُوٓءَ ٱلْحِسَابِ ﴿٢١﴾ وَٱلَّذِينَ صَبَرُوا۟ ٱبْتِغَآءَ وَجْهِ رَبِّهِمْ
وَأَقَامُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَأَنفَقُوا۟ مِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ سِرًّا وَعَلَانِيَةً وَيَدْرَءُونَ
بِٱلْحَسَنَةِ ٱلسَّيِّئَةَ أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ عُقْبَى ٱلدَّارِ ﴿٢٢﴾ جَنَّٰتُ عَدْنٍ يَدْخُلُونَهَا
وَمَن صَلَحَ مِنْ ءَابَآئِهِمْ وَأَزْوَٰجِهِمْ وَذُرِّيَّٰتِهِمْ ۖ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَدْخُلُونَ
عَلَيْهِم مِّن كُلِّ بَابٍ ﴿٢٣﴾ سَلَٰمٌ عَلَيْكُم بِمَا صَبَرْتُمْ ۚ فَنِعْمَ عُقْبَى ٱلدَّارِ ﴿٢٤﴾
وَٱلَّذِينَ يَنقُضُونَ عَهْدَ ٱللَّهِ مِنۢ بَعْدِ مِيثَٰقِهِۦ وَيَقْطَعُونَ
مَآ أَمَرَ ٱللَّهُ بِهِۦٓ أَن يُوصَلَ وَيُفْسِدُونَ فِى ٱلْأَرْضِ أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمُ
ٱللَّعْنَةُ وَلَهُمْ سُوٓءُ ٱلدَّارِ ﴿٢٥﴾ ٱللَّهُ يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ
وَيَقْدِرُ ۚ وَفَرِحُوا۟ بِٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَمَا ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا فِى ٱلْءَاخِرَةِ إِلَّا
مَتَٰعٌ ﴿٢٦﴾ وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لَوْلَآ أُنزِلَ عَلَيْهِ ءَايَةٌ مِّن رَّبِّهِۦ ۚ قُلْ
إِنَّ ٱللَّهَ يُضِلُّ مَن يَشَآءُ وَيَهْدِىٓ إِلَيْهِ مَنْ أَنَابَ ﴿٢٧﴾ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟
وَتَطْمَئِنُّ قُلُوبُهُم بِذِكْرِ ٱللَّهِ ۗ أَلَا بِذِكْرِ ٱللَّهِ تَطْمَئِنُّ ٱلْقُلُوبُ ﴿٢٨﴾

(19) Yanzu wanda ya san cewa abin da aka saukar maka daga Ubangijinka gaskiya ne (zai zama) kamar wanda yake shi makaho ne? Lalle ma'abota hankali ne kaɗai ke wa'azantuwa
(20) (Su ne) waɗanda suke cika alƙawarin Allah kuma ba sa warware alƙawarin
(21) Waɗanda kuma suke sadar da abin da Allah Ya yi umarni a sadar da shi (na zumunci), suke kuma tsoron Ubangijinsu, kuma suke tsoron mummunan hisabi
(22) Waɗanda kuma suka yi haƙuri don neman yardar Ubangijnsu, suka kuma tsai da salla, kuma suka ciyar daga abin da Muka arzuta su da shi a ɓoye da sarari, suke kuma ingije mummunan aiki da kyakkyawa, waɗannan suna da (kyakkyawar) makoma ta gidan (Aljanna)
(23) Gidajen Aljanna na dawwama, za su shiga su da waɗanda suka kyautata (aiki) daga iyayensu da matansu da kuma zuriyarsu; mala'iku kuma za su riƙa shigowa wurinsu ta kowace ƙofa
(24) (Suna ce musu): "Aminci ya tabbata a gare ku saboda haƙurin da kuka yi. To madalla da gida na ƙarshe (watau Aljanna)"
(25) Waɗanda kuma suke warware alƙawarin Allah bayan sun ƙulla shi, suke kuma yanke abin da Allah Ya yi umarni a sadar da shi, kuma suke ɓarna a bayan ƙasa, waɗannan la'ana ta tabbata a gare su kuma suna da (sakamakon) mummunan gida (shi ne Jahannama)
(26) Allah ne Yake shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, Yake kuma ƙuntatawa (ga wanda Ya ga dama. (Kafirai) kuma sun yi farin ciki da rayuwar duniya, rayuwar duniya kuwa ba komai ba ce illa ɗan jin daɗi kaɗan dangane da na lahira
(27) Waɗanda suka kafirta kuma suna cewa: "Me ya hana a saukar masa da aya daga Ubangijinsa?" Ka ce: "Lalle Allah Yana ɓatar da wanda Ya ga dama, Yana kuma shiryar da wanda ya koma gare Shi
(28) "(Su ne) waɗanda suka yi imani, zukatansu kuma suna nutsuwa da ambaton Allah. Ku saurara, da ambaton Allah ne zukata suke nutsuwa

ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ طُوبَىٰ لَهُمْ وَحُسْنُ مَـَٔابٍ ﴿٢٩﴾
كَذَٰلِكَ أَرْسَلْنَٰكَ فِىٓ أُمَّةٍ قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِهَآ أُمَمٌ لِّتَتْلُوَا۟
عَلَيْهِمُ ٱلَّذِىٓ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ وَهُمْ يَكْفُرُونَ بِٱلرَّحْمَٰنِ ۚ قُلْ هُوَ رَبِّى
لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ عَلَيْهِ تَوَكَّلْتُ وَإِلَيْهِ مَتَابِ ﴿٣٠﴾ وَلَوْ أَنَّ قُرْءَانًا
سُيِّرَتْ بِهِ ٱلْجِبَالُ أَوْ قُطِّعَتْ بِهِ ٱلْأَرْضُ أَوْ كُلِّمَ بِهِ ٱلْمَوْتَىٰ ۗ
بَل لِّلَّهِ ٱلْأَمْرُ جَمِيعًا ۗ أَفَلَمْ يَاْيْـَٔسِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَن لَّوْ يَشَآءُ
ٱللَّهُ لَهَدَى ٱلنَّاسَ جَمِيعًا ۗ وَلَا يَزَالُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ تُصِيبُهُم
بِمَا صَنَعُوا۟ قَارِعَةٌ أَوْ تَحُلُّ قَرِيبًا مِّن دَارِهِمْ حَتَّىٰ يَأْتِىَ وَعْدُ
ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُخْلِفُ ٱلْمِيعَادَ ﴿٣١﴾ وَلَقَدِ ٱسْتُهْزِئَ بِرُسُلٍ مِّن
قَبْلِكَ فَأَمْلَيْتُ لِلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ثُمَّ أَخَذْتُهُمْ ۖ فَكَيْفَ كَانَ
عِقَابِ ﴿٣٢﴾ أَفَمَنْ هُوَ قَآئِمٌ عَلَىٰ كُلِّ نَفْسٍۭ بِمَا كَسَبَتْ ۗ وَجَعَلُوا۟
لِلَّهِ شُرَكَآءَ ۚ قُلْ سَمُّوهُمْ ۚ أَمْ تُنَبِّـُٔونَهُۥ بِمَا لَا يَعْلَمُ فِى ٱلْأَرْضِ أَم
بِظَٰهِرٍ مِّنَ ٱلْقَوْلِ ۗ بَلْ زُيِّنَ لِلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مَكْرُهُمْ وَصُدُّوا۟ عَنِ
ٱلسَّبِيلِ ۗ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنْ هَادٍ ﴿٣٣﴾ لَّهُمْ عَذَابٌ فِى ٱلْحَيَوٰةِ
ٱلدُّنْيَا ۖ وَلَعَذَابُ ٱلْـَٔاخِرَةِ أَشَقُّ ۖ وَمَا لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن وَاقٍ ﴿٣٤﴾

(29) "Waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, to farin ciki ya tabbata a gare su da kuma kyakkyawar makoma."
(30) (Kamar haka Muka aiko ka cikin al'umma wadda tuni wasu al'ummun sun wuce kafinta, don ka karanta musu abin da Muka yi maka wahayinsa, alhali kuwa su suna kafirce wa Arrahamanu[1]. Ka ce: "Shi ne Ubangijina, babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, gare Shi kawai na dogara, kuma gare Shi kawai tubata take."
(31) Da a ce akwai wani abin karantawa da za a gusar da duwatsu da shi, ko kuma a keta ƙasa da shi, ko kuma a yi magana da matattu da shi, (to da wannan Alƙur'anin ne). Bari dai, dukkanin al'amari gaba ɗaya na Allah ne. Shin waɗanda suka yi imani ba su san da cewa da Allah Ya ga dama da Ya shiryi mutane gaba ɗaya ba? Kafirai kuwa azaba ba za ta daina samun su ba saboda abin da suka aikata, ko kuwa ta faɗo kusa da gidajensu har sai alƙawarin Allah ya zo. Lalle Allah ba Ya saɓa alƙawari
(32) Haƙiƙa an yi wa manzannin da suka gabace ka izgili, sai Na yi wa waɗanda suka kafirta talala, sannan Na damƙe su. To yaya uƙubata ta kasance (a gare su)?
(33)Yanzu wanda Yake tsaye a kan kula da kowane rai game da abin da ya aikata, (zai zama daidai da wanda ba haka ba?) Sun kuma sanya wa Allah abokan tarayya. Ka ce: (da su) "Ku faɗa min sunayensu. Ko kuwa kuna ba Shi labarin abin da bai sani ba ne a bayan ƙasa, ko kuma dai kun riƙe wata ɓatacciyar magana ce?" Bari dai; an dai ƙawata wa kafirai makircinsu ne kawai, aka kuma toshe musu hanyar (Allah). Wanda kuwa Allah Ya ɓatar to ba shi da wani mai shiryarwa
(34) Suna da wata azaba a rayuwar duniya; kuma lalle azabar lahira ita ta fi tsanani; ba su kuwa da wani mai kare su daga (azabar) Allah

(1) Kafiran Kuraishawa suna ƙyamar su siffanta Allah da suna Arrahman, watau Mai rahma, kamar yadda ya zo a cikin Suratul Furƙan aya ta 60.

مَّثَلُ ٱلْجَنَّةِ ٱلَّتِى وُعِدَ ٱلْمُتَّقُونَ ۖ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ ۖ
أُكُلُهَا دَآئِمٌ وَظِلُّهَا ۚ تِلْكَ عُقْبَى ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوا۟ ۖ وَّعُقْبَى
ٱلْكَٰفِرِينَ ٱلنَّارُ ﴿٣٥﴾ وَٱلَّذِينَ ءَاتَيْنَٰهُمُ ٱلْكِتَٰبَ يَفْرَحُونَ
بِمَآ أُنزِلَ إِلَيْكَ ۖ وَمِنَ ٱلْأَحْزَابِ مَن يُنكِرُ بَعْضَهُۥ ۚ قُلْ إِنَّمَآ
أُمِرْتُ أَنْ أَعْبُدَ ٱللَّهَ وَلَآ أُشْرِكَ بِهِۦٓ ۚ إِلَيْهِ أَدْعُوا۟ وَإِلَيْهِ مَـَٔابِ
﴿٣٦﴾ وَكَذَٰلِكَ أَنزَلْنَٰهُ حُكْمًا عَرَبِيًّا ۚ وَلَئِنِ ٱتَّبَعْتَ أَهْوَآءَهُم بَعْدَ
مَا جَآءَكَ مِنَ ٱلْعِلْمِ ۙ مَا لَكَ مِنَ ٱللَّهِ مِن وَلِىٍّ وَلَا وَاقٍ ﴿٣٧﴾ وَلَقَدْ
أَرْسَلْنَا رُسُلًا مِّن قَبْلِكَ وَجَعَلْنَا لَهُمْ أَزْوَٰجًا وَذُرِّيَّةً ۚ وَمَا كَانَ
لِرَسُولٍ أَن يَأْتِىَ بِـَٔايَةٍ إِلَّا بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۗ لِكُلِّ أَجَلٍ كِتَابٌ ﴿٣٨﴾
يَمْحُوا۟ ٱللَّهُ مَا يَشَآءُ وَيُثْبِتُ ۖ وَعِندَهُۥٓ أُمُّ ٱلْكِتَٰبِ ﴿٣٩﴾ وَإِن مَّا
نُرِيَنَّكَ بَعْضَ ٱلَّذِى نَعِدُهُمْ أَوْ نَتَوَفَّيَنَّكَ فَإِنَّمَا عَلَيْكَ ٱلْبَلَٰغُ
وَعَلَيْنَا ٱلْحِسَابُ ﴿٤٠﴾ أَوَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّا نَأْتِى ٱلْأَرْضَ نَنقُصُهَا
مِنْ أَطْرَافِهَا ۚ وَٱللَّهُ يَحْكُمُ لَا مُعَقِّبَ لِحُكْمِهِۦ ۚ وَهُوَ سَرِيعُ
ٱلْحِسَابِ ﴿٤١﴾ وَقَدْ مَكَرَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ فَلِلَّهِ ٱلْمَكْرُ جَمِيعًا ۖ
يَعْلَمُ مَا تَكْسِبُ كُلُّ نَفْسٍ ۗ وَسَيَعْلَمُ ٱلْكُفَّٰرُ لِمَنْ عُقْبَى ٱلدَّارِ ﴿٤٢﴾

(35) Misalin Aljannar nan da aka yi wa masu takawa alkawari da ita; koramu ne suke gudana ta karkashinta; abincinta kuma mai dawwama ne da kuma inuwarta. Wannan shi ne makomar wadanda suka kiyaye dokokin Allah; makomar kafirai kuma ita ce wuta

(36) Wadanda kuwa Muka bai wa littafi (muminansu) suna farin ciki da abin da aka saukar maka; akwai kuma wasu daga kungiyoyi wadanda suke musun wani sashi nasa. Ka ce: "Ni dai an umarce ni ne kawai da in bauta wa Allah, kada kuma in tara wani abu da Shi. Kuma zuwa gare Shi kawai nake kira, wurinsa ne kawai kuma makomata."

(37) Kamar haka Muka saukar da shi (Alkur'ani), ya zama hukunci, da harshen Larabci. Lalle kuma idan ka bi son ransu bayan abin da ya zo maka na ilimi, to ba ka da wani majibinci ko mai kariya daga (azabar) Allah

(38) Hakika kuma Mun aiko manzanni a gabaninka, Muka kuma ba su matan aure da zurriya. Bai kuma kamata ba ga wani annabi ya zo da wata aya (da za a neme shi da ya kawo ta) sai da izinin Allah. Kuma kowane lokaci yana nan a rubuce


(39) Allah Yana shafe abin da ya ga dama, Yana kuma tabbatar (da abin da ya ga dama); kuma a wurinsa asalin littafi yake[1]

(40)Ko dai Mu nuna maka irin sashin abin da Muke yi musu gargadi da aukuwarsa, ko kuma Mu karbi ranka (kafin lokacin), abin da yake kanka kawai shi ne isar da aike, Mu kuma hisabi yana a kanmu

(41) Yanzu ba sa ganin cewa Muna zaike wa kasa Muna ta cinye iyakokinta[2]? Allah ne Mai yin hukunci, babu kuma mai yin gyara ga hukuncinsa. Shi ne kuma Mai saurin yin hisabi(42) Hakika kuma wadanda suke gabaninsu sun kulla makirci, (sakamakon) kulle-kulle dukkaninsa ga Allah yake; Yana sane da abin da kowane rai yake aikatawa. Ba da dadewa ba kuma kafirai za su san wane ne mai kyakkyawan gidan (karshe)

(1) Watau Lauhul Mahfuzu, littafin da Allah ya rubuta komai a cikinsa.

(2) Watau Musulmi suna ta samun nasara a kansu, suna ta cinye garuruwansu da yaki.


وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لَسْتَ مُرْسَلًا ۚ قُلْ كَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدًۢا
بَيْنِى وَبَيْنَكُمْ وَمَنْ عِندَهُۥ عِلْمُ ٱلْكِتَٰبِ ﴿٤٣﴾
سُورَةُ إِبْرَٰهِيمَ
بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
الٓر ۚ كِتَٰبٌ أَنزَلْنَٰهُ إِلَيْكَ لِتُخْرِجَ ٱلنَّاسَ مِنَ ٱلظُّلُمَٰتِ
إِلَى ٱلنُّورِ بِإِذْنِ رَبِّهِمْ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلْعَزِيزِ ٱلْحَمِيدِ ﴿١﴾
ٱللَّهِ ٱلَّذِى لَهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۗ وَوَيْلٌ
لِّلْكَٰفِرِينَ مِنْ عَذَابٍ شَدِيدٍ ﴿٢﴾ ٱلَّذِينَ يَسْتَحِبُّونَ
ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا عَلَى ٱلْءَاخِرَةِ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ
ٱللَّهِ وَيَبْغُونَهَا عِوَجًا ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ فِى ضَلَٰلٍۭ بَعِيدٍ ﴿٣﴾ وَمَآ
أَرْسَلْنَا مِن رَّسُولٍ إِلَّا بِلِسَانِ قَوْمِهِۦ لِيُبَيِّنَ لَهُمْ ۖ
فَيُضِلُّ ٱللَّهُ مَن يَشَآءُ وَيَهْدِى مَن يَشَآءُ ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ
ٱلْحَكِيمُ ﴿٤﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَآ أَنْ أَخْرِجْ
قَوْمَكَ مِنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ وَذَكِّرْهُم بِأَيَّىٰمِ
ٱللَّهِ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّكُلِّ صَبَّارٍ شَكُورٍ ﴿٥﴾

(43) Kafirai kuma suna cewa: “Kai ba manzo ba ne.” Ka ce (da su): “Allah Ya isa shaida tsakanina da ku, da kuma wanda yake da ilimin Littafi[1].”

Sura Ibrahim

(1) ALIF LAM RA[1]. Littafi ne da Muka saukar maka da shi, don ka fitar da mutane daga duffai zuwa ga haske, da izinin Ubangijinsu zuwa ga tafarkin (Allah) Mabuwayi, Abin godiya

(2) (Watau) Allah, Wanda abin da yake cikin sammai da na cikin ƙasa duka nasa ne. Bone na wata azaba mai tsanani kuma ya tabbatta ga kafirai

(3) Waɗanda suke fifita son rayuwar duniya a kan lahira, suke kuma hanawa (a bi) hanyar Allah, kuma suke neman ta zama karkatacciya. To waɗannan suna cikin ɓata mai nisa

(4) Ba Mu taɓa aiko wani manzo ba kuwa sai da harshen mutanensa don ya yi musu bayani; sannan Allah Yana ɓatar da wanda ya ga dama, ya kuma shiryar da wanda ya ga dama. Shi ne kuwa Mabuwayi, Mai hikima

(5) Haƙiƙa kuma Mun aiko Musa da ayoyinmu cewa: “Ka fitar da mutananka daga duffai zuwa ga haske, kuma ka tunatar da su ni’imomin Allah (da ya yi musu).” Lalle game da wannan da akwai ayoyi ga duk wani mai yawan haƙuri, mai yawan godiya

(1) Watau malaman Ahlulkitabi waɗanda suka musulunta suka shaida da manzancinsa, suka yi imani da shi.

(2) Duba Suratul Baƙara aya ta 1, hashiya ta 8.

وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِ ٱذْكُرُوا۟ نِعْمَةَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ
إِذْ أَنجَىٰكُم مِّنْ ءَالِ فِرْعَوْنَ يَسُومُونَكُمْ سُوٓءَ ٱلْعَذَابِ
وَيُذَبِّحُونَ أَبْنَآءَكُمْ وَيَسْتَحْيُونَ نِسَآءَكُمْ ۚ وَفِى
ذَٰلِكُم بَلَآءٌ مِّن رَّبِّكُمْ عَظِيمٌ ﴿٦﴾ وَإِذْ تَأَذَّنَ رَبُّكُمْ
لَئِن شَكَرْتُمْ لَأَزِيدَنَّكُمْ ۖ وَلَئِن كَفَرْتُمْ إِنَّ عَذَابِى
لَشَدِيدٌ ﴿٧﴾ وَقَالَ مُوسَىٰٓ إِن تَكْفُرُوٓا۟ أَنتُمْ وَمَن فِى
ٱلْأَرْضِ جَمِيعًا فَإِنَّ ٱللَّهَ لَغَنِىٌّ حَمِيدٌ ﴿٨﴾ أَلَمْ يَأْتِكُمْ نَبَؤُا۟
ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ قَوْمِ نُوحٍ وَعَادٍ وَثَمُودَ وَٱلَّذِينَ
مِنۢ بَعْدِهِمْ لَا يَعْلَمُهُمْ إِلَّا ٱللَّهُ ۖ جَآءَتْهُمْ رُسُلُهُم
بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَرَدُّوٓا۟ أَيْدِيَهُمْ فِىٓ أَفْوَٰهِهِمْ وَقَالُوٓا۟ إِنَّا كَفَرْنَا
بِمَآ أُرْسِلْتُم بِهِۦ وَإِنَّا لَفِى شَكٍّ مِّمَّا تَدْعُونَنَآ إِلَيْهِ مُرِيبٍ ﴿٩﴾
* قَالَتْ رُسُلُهُمْ أَفِى ٱللَّهِ شَكٌّ فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ
يَدْعُوكُمْ لِيَغْفِرَ لَكُم مِّن ذُنُوبِكُمْ وَيُؤَخِّرَكُمْ إِلَىٰٓ أَجَلٍ
مُّسَمًّى ۚ قَالُوٓا۟ إِنْ أَنتُمْ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُنَا تُرِيدُونَ أَن تَصُدُّونَا
عَمَّا كَانَ يَعْبُدُ ءَابَآؤُنَا فَأْتُونَا بِسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿١٠﴾

(6) Kuma (ka tuna) lokacin da Musa ya ce da mutanensa: “Ku tuna ni’imar Allah a gare ku lokacin da Ya tserar da ku daga mutanen Fir’auna, suna gana muku azaba, suna kuma yanyanka ‘ya’yanku, kuma suna raya matayenku. A game da wannan da akwai bala’i mai girma daga Ubangijinku

(7) “Kuma (ku tuna) lokacin da Ubangijinku ya sanar da ku: “Lalle idan kuka gode wa (ni’imata) tabbas zan ƙara muku; idan kuwa kuka butulce, to lalle azabata tabbas mai tsanani ce.”

(8) Musa kuma ya ce: “Idan kuka kafirce, ku da waɗanda suke a bayan ƙasa baki ɗaya, to lalle Allah tabbas Mawadaci ne, Sha-yabo.”

(9) Wai yanzu labarin waɗanda suka gabace ku bai zo muku ba na mutanen Nuhu da Adawa da Samudawa da waɗanda (suka zo) daga bayansu? Ba wanda ya san iyakarsu sai Allah. Manzanninsu sun zo musu da hujjoji bayyanannu, amma sai suka rika cizon hannayensu (saboda haushi), suka kuma ce: “Lalle mu kam mun kafirta da abin da aka aiko ku da shi, lalle kuma muna cikin matuƙar shakka game abin da kuke kiran mu zuwa gare shi.”

(10) Mazanninsu suka ce: “Yanzu kuwa ashe akwai wata shakka game da Allah, Maƙagin sammai da ƙasa? Yana kiran ku ne don ya gafarta muku zunubanku kuma ya saurara muku har zuwa wani lokaci ƙayyadajje.” Suka ce: “Ku ba wasu ba ne daban in ban da mutane kamar mu, kuna so ne ku hana mu bin abin da iyanenmu suka kasance suna bauta wa, to sai ku kawo mana hujjoji bayyanannu.”

قَالَتْ لَهُمْ رُسُلُهُمْ إِن نَّحْنُ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ
يَمُنُّ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ ۖ وَمَا كَانَ لَنَآ أَن نَّأْتِيَكُم
بِسُلْطَٰنٍ إِلَّا بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ ٱلْمُؤْمِنُونَ
﴿١١﴾ وَمَا لَنَآ أَلَّا نَتَوَكَّلَ عَلَى ٱللَّهِ وَقَدْ هَدَىٰنَا سُبُلَنَا ۚ وَلَنَصْبِرَنَّ
عَلَىٰ مَآ ءَاذَيْتُمُونَا ۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ ٱلْمُتَوَكِّلُونَ
﴿١٢﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لِرُسُلِهِمْ لَنُخْرِجَنَّكُم مِّنْ أَرْضِنَآ
أَوْ لَتَعُودُنَّ فِى مِلَّتِنَا ۖ فَأَوْحَىٰٓ إِلَيْهِمْ رَبُّهُمْ لَنُهْلِكَنَّ
ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٣﴾ وَلَنُسْكِنَنَّكُمُ ٱلْأَرْضَ مِنۢ بَعْدِهِمْ ۚ
ذَٰلِكَ لِمَنْ خَافَ مَقَامِى وَخَافَ وَعِيدِ ﴿١٤﴾ وَٱسْتَفْتَحُوا۟
وَخَابَ كُلُّ جَبَّارٍ عَنِيدٍ ﴿١٥﴾ مِّن وَرَآئِهِۦ جَهَنَّمُ وَيُسْقَىٰ
مِن مَّآءٍ صَدِيدٍ ﴿١٦﴾ يَتَجَرَّعُهُۥ وَلَا يَكَادُ يُسِيغُهُۥ وَيَأْتِيهِ
ٱلْمَوْتُ مِن كُلِّ مَكَانٍ وَمَا هُوَ بِمَيِّتٍ ۖ وَمِن وَرَآئِهِۦ
عَذَابٌ غَلِيظٌ ﴿١٧﴾ مَّثَلُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِرَبِّهِمْ ۖ أَعْمَٰلُهُمْ
كَرَمَادٍ ٱشْتَدَّتْ بِهِ ٱلرِّيحُ فِى يَوْمٍ عَاصِفٍ ۖ لَّا يَقْدِرُونَ
مِمَّا كَسَبُوا۟ عَلَىٰ شَىْءٍ ۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلضَّلَٰلُ ٱلْبَعِيدُ ﴿١٨﴾

(11) Manzanninsu suka ce: “Mu ba kowa ba ne in ban da mutane kamarku, sai dai Allah Yana yin baiwa ga wanda Ya ga dama ne daga bayinsa, kuma ba zai yiwu ba a gare mu mu zo muku da wata hujja sai dai da izinin Allah. Muminai kuwa lalle su dogara ga Allah kawai
(12) “Kuma me zai hana mu mu dogara ga Allah, alhali kuwa haƙiƙa Ya shiryar da mu hanyoyinmu? Lalle kuwa tabbas za mu yi haƙuri bisa irin cutar mu da kuka yi. Masu dogaro kuma sai su dogara ga Allah kaɗai.”
(13) Waɗanda suka kafirta kuma suka ce da manzanninsu: “Lalle ba makawa za mu fitar da ku daga ƙasarmu, ko kuwa lalle ku komo cikin addininmu. Sai Ubangijinsu ya aiko musu cewa: “Lalle za Mu hallaka azzalumai
(14) “Kuma tabbas za mu zaunar da ku ƙasar (tasu) a bayansu. Wannan kuwa sai ga wanda ya ji tsoron tsayuwa a gabana ya kuma ji tsoron narkona.”
(15) Sai kuma (manzannin) suka nemi nasarar (Allah), kuma (a ƙarshenta) duk wani mai nuna isa mai taurin kai ya hallaka
(16) A gabansa Jahannama ce (take jiran sa), za a kuma shayar da shi ruwan mugunya
(17) Yana kwankwaɗar sa, ba kuwa zai ji daɗin haɗiyarsa ba, mutuwa kuma za ta zo masa ko ta ina, ba kuwa zai mutu ba; kuma a gabansa ga azaba mai kauri
(18) Misalin waɗanda suka kafirce wa Ubangijnsu; ayyukansu sun yi kama da toka wadda iska mai tsananin ƙarfi ta kwasa a wata rana mai guguwa; ba za su sami iko a kan komai ba dangane da abin da suka aikata (na kirki). Wannan shi ne ɓata mai nisa

أَلَمْ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ بِٱلْحَقِّ ۚ إِن يَشَأْ
يُذْهِبْكُمْ وَيَأْتِ بِخَلْقٍ جَدِيدٍ ﴿١٩﴾ وَمَا ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ بِعَزِيزٍ
﴿٢٠﴾ وَبَرَزُوا۟ لِلَّهِ جَمِيعًا فَقَالَ ٱلضُّعَفَٰٓؤُا۟ لِلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُوٓا۟
إِنَّا كُنَّا لَكُمْ تَبَعًا فَهَلْ أَنتُم مُّغْنُونَ عَنَّا مِنْ عَذَابِ ٱللَّهِ
مِن شَىْءٍ ۚ قَالُوا۟ لَوْ هَدَىٰنَا ٱللَّهُ لَهَدَيْنَٰكُمْ ۖ سَوَآءٌ عَلَيْنَآ
أَجَزِعْنَآ أَمْ صَبَرْنَا مَا لَنَا مِن مَّحِيصٍ ﴿٢١﴾ وَقَالَ ٱلشَّيْطَٰنُ لَمَّا
قُضِىَ ٱلْأَمْرُ إِنَّ ٱللَّهَ وَعَدَكُمْ وَعْدَ ٱلْحَقِّ وَوَعَدتُّكُمْ
فَأَخْلَفْتُكُمْ ۖ وَمَا كَانَ لِىَ عَلَيْكُم مِّن سُلْطَٰنٍ إِلَّآ
أَن دَعَوْتُكُمْ فَٱسْتَجَبْتُمْ لِى ۖ فَلَا تَلُومُونِى وَلُومُوٓا۟ أَنفُسَكُم ۖ
مَّآ أَنَا۠ بِمُصْرِخِكُمْ وَمَآ أَنتُم بِمُصْرِخِىَّ ۖ إِنِّى كَفَرْتُ
بِمَآ أَشْرَكْتُمُونِ مِن قَبْلُ ۗ إِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ لَهُمْ عَذَابٌ
أَلِيمٌ ﴿٢٢﴾ وَأُدْخِلَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ جَنَّٰتٍ
تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا بِإِذْنِ رَبِّهِمْ ۖ تَحِيَّتُهُمْ
فِيهَا سَلَٰمٌ ﴿٢٣﴾ أَلَمْ تَرَ كَيْفَ ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلًا كَلِمَةً طَيِّبَةً
كَشَجَرَةٍ طَيِّبَةٍ أَصْلُهَا ثَابِتٌ وَفَرْعُهَا فِى ٱلسَّمَآءِ ﴿٢٤﴾

(19) Ashe ba ka ga cewa, lalle Allah Ya halicci sammai da ƙasa kan gaskiya ba? Idan Ya ga dama sai Ya hallakar da ku Ya kuma zo da wata halitta sabuwa
(20) Wannan kuwa ba abin da zai gagari Allah ba ne
(21) Suka kuma fito gaba ɗaya a gaban Allah (ranar alƙiyama), sai raunanan suka ce da waɗanda suka yi girman kai: "Lalle mu mun zamanto mabiya a gare ku, to ko za ku maganta mana wani abu daga azabar Allah?" Suka ce: "Da Allah Ya shirye mu da lalle mun shiryar da ku; duka ɗaya ne gare mu ko mun yi raki ko mun yi haƙuri (duka dai) ba mu da wata maguda."
(22) Shaiɗan kuma lokacin da aka gama hukunci ya ce: "Lalle Allah Ya yi muku alƙawari na gaskiya, ni kuma na yi muku alƙawari sai na saɓa muku. To ba ni da wani ƙarfi da na nuna muku, sai dai na yi kiran ku ne sai kuka amsa mini; to kada ku zarge ni, ku zargi kanku; ni ba zan taimake ku ba, ku kuma ba za ku taimake ni ba. Lalle ni na riga na kafirta da abin da kuka yi tarayya da ni a kansa tun a da can. Lalle azzalumai suna da (sakamakon) azaba mai raɗaɗi."
(23) Aka kuma shigar da waɗanda suka yi imani, suka kuma yi aiki nagari gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu da izinin Ubangijinsu; gaisuwarsu a cikinsu ita ce: "Aminci (ya tabbata a gare ku)."
(24) Shin ba ka ga yadda Allah Ya ba da misali ba? Daddaɗar kalma(1) kamar daddaɗar bishiya ce(2) wadda tushenta kafaffe ne (a ƙasa) reshenta kuma yana sama

(1) Daddaɗar kalma ita ce kalmar shahada, watau shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah.

(2) Daddaɗar bishiya kuwa ita ce bishiyar dabino. A nan ana nufin mumini. Kalmar shahada tana kafa tushenta a ciki zuciyar mumini.

تُؤْتِيٓ أُكُلَهَا كُلَّ حِينٍۭ بِإِذْنِ رَبِّهَا ۗ وَيَضْرِبُ ٱللَّهُ ٱلْأَمْثَالَ
لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿٢٥﴾ وَمَثَلُ كَلِمَةٍ خَبِيثَةٍ
كَشَجَرَةٍ خَبِيثَةٍ ٱجْتُثَّتْ مِن فَوْقِ ٱلْأَرْضِ مَا لَهَا مِن
قَرَارٍ ﴿٢٦﴾ يُثَبِّتُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱلْقَوْلِ ٱلثَّابِتِ فِى ٱلْحَيَوٰةِ
ٱلدُّنْيَا وَفِى ٱلْءَاخِرَةِ ۖ وَيُضِلُّ ٱللَّهُ ٱلظَّٰلِمِينَ ۚ وَيَفْعَلُ ٱللَّهُ
مَا يَشَآءُ ﴿٢٧﴾ ۞ أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ بَدَّلُوا۟ نِعْمَتَ ٱللَّهِ كُفْرًا
وَأَحَلُّوا۟ قَوْمَهُمْ دَارَ ٱلْبَوَارِ ﴿٢٨﴾ جَهَنَّمَ يَصْلَوْنَهَا ۖ وَبِئْسَ
ٱلْقَرَارُ ﴿٢٩﴾ وَجَعَلُوا۟ لِلَّهِ أَندَادًا لِّيُضِلُّوا۟ عَن سَبِيلِهِۦ ۗ قُلْ
تَمَتَّعُوا۟ فَإِنَّ مَصِيرَكُمْ إِلَى ٱلنَّارِ ﴿٣٠﴾ قُل لِّعِبَادِىَ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ يُقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُنفِقُوا۟ مِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ سِرًّا وَعَلَانِيَةً
مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِىَ يَوْمٌ لَّا بَيْعٌ فِيهِ وَلَا خِلَٰلٌ ﴿٣١﴾ ٱللَّهُ ٱلَّذِى
خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجَ
بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزْقًا لَّكُمْ ۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلْفُلْكَ لِتَجْرِىَ
فِى ٱلْبَحْرِ بِأَمْرِهِۦ ۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلْأَنْهَٰرَ ﴿٣٢﴾ وَسَخَّرَ لَكُمُ
ٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ دَآئِبَيْنِ ۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ ﴿٣٣﴾

(25) Tana bayar da ‘ya’yanta ko da yaushe da izinin Ubangijinta. Allah kuwa Yana ba da misalai ne ga mutane don su wa’azantu
(26) Misalin kuma mummunar kalma kamar mummunar bishiya ce da aka tumɓuke daga kan ƙasa, ba ta da wata matabbata
(27) Allah Yana tabbatar da waɗanda suka yi imani a kan magana tabbatacciya a rayuwar duniya da kuma a lahira; Yana kuma ɓatar da azzalumai. Allah kuma Yana aikata abin da Ya ga dama (Shin ba ka ga waɗanda suka musanya ni’imar Allah da kafirci ba[1], suka kuma jefa mutanensu gidan hallaka?
(29) (Watau) Jahannama, za su shige ta; makoma kuwa ta munana
(30) Sun sanya wa Allah abokan tarayya don su ɓatar (da mutane) daga hanyarsa. Ka ce: “Ku ji daɗi (kaɗan a duniya), to lalle makomarku wuta ce!”
(31) Ka ce da bayina waɗanda suka yi imani, su tsayar da salla kuma su ciyar daga abin da Muka arzuta su da shi, a ɓoye da sarari tun kafin zuwan ranar da babu ciniki a cikinta, kuma babu abota
(32) Allah ne Wanda Ya halicci sammai da ƙasa, Ya kuma saukar da ruwa daga sama, sai Ya fitar da ‘ya’yan itace don arzuta ku; Ya kuma hore muku jiragen ruwa don ku yi tafiya a cikin kogi da umarninsa, Ya kuma hore muku ƙoramu
(33) Ya kuma hore muku rana da wata tutur; Ya kuma hore muku dare da rana

(1) Su ne kafiran Kuraishawa.

وَءَاتَىٰكُم مِّن كُلِّ مَا سَأَلْتُمُوهُ ۚ وَإِن تَعُدُّوا۟ نِعْمَتَ ٱللَّهِ
لَا تُحْصُوهَآ ۗ إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لَظَلُومٌ كَفَّارٌ ﴿٣٤﴾ وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ
رَبِّ ٱجْعَلْ هَٰذَا ٱلْبَلَدَ ءَامِنًا وَٱجْنُبْنِى وَبَنِىَّ أَن نَّعْبُدَ
ٱلْأَصْنَامَ ﴿٣٥﴾ رَبِّ إِنَّهُنَّ أَضْلَلْنَ كَثِيرًا مِّنَ ٱلنَّاسِ ۖ فَمَن
تَبِعَنِى فَإِنَّهُۥ مِنِّى ۖ وَمَنْ عَصَانِى فَإِنَّكَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٣٦﴾ رَّبَّنَآ
إِنِّىٓ أَسْكَنتُ مِن ذُرِّيَّتِى بِوَادٍ غَيْرِ ذِى زَرْعٍ عِندَ بَيْتِكَ
ٱلْمُحَرَّمِ رَبَّنَا لِيُقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ فَٱجْعَلْ أَفْـِٔدَةً مِّنَ ٱلنَّاسِ
تَهْوِىٓ إِلَيْهِمْ وَٱرْزُقْهُم مِّنَ ٱلثَّمَرَٰتِ لَعَلَّهُمْ يَشْكُرُونَ
﴿٣٧﴾ رَبَّنَآ إِنَّكَ تَعْلَمُ مَا نُخْفِى وَمَا نُعْلِنُ ۗ وَمَا يَخْفَىٰ عَلَى ٱللَّهِ
مِن شَىْءٍ فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا فِى ٱلسَّمَآءِ ﴿٣٨﴾ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِى
وَهَبَ لِى عَلَى ٱلْكِبَرِ إِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ ۚ إِنَّ رَبِّى لَسَمِيعُ
ٱلدُّعَآءِ ﴿٣٩﴾ رَبِّ ٱجْعَلْنِى مُقِيمَ ٱلصَّلَوٰةِ وَمِن ذُرِّيَّتِى ۚ رَبَّنَا
وَتَقَبَّلْ دُعَآءِ ﴿٤٠﴾ رَبَّنَا ٱغْفِرْ لِى وَلِوَٰلِدَىَّ وَلِلْمُؤْمِنِينَ
يَوْمَ يَقُومُ ٱلْحِسَابُ ﴿٤١﴾ وَلَا تَحْسَبَنَّ ٱللَّهَ غَٰفِلًا عَمَّا يَعْمَلُ
ٱلظَّٰلِمُونَ ۚ إِنَّمَا يُؤَخِّرُهُمْ لِيَوْمٍ تَشْخَصُ فِيهِ ٱلْأَبْصَٰرُ ﴿٤٢﴾

(34) Ya kuma ba ku daga duk abin da kuka roƙe Shi. In da za ku ƙirga ni'imomin Allah to ba za ku iya ƙididdige su ba. Lalle mutum mai yawan zalunci ne mai yawan butulci

(35) (Ka tuna) kuma lokacin da Ibrahimu ya ce: "Ya Ubangijina, Ka sanya wannan gari (Makka) ya zama amintacce, kuma Ka nesantar da ni da 'ya'yana daga bauta wa gumaka

(36) "Ya Ubangijina, lalle su (gumakan) sun ɓatar da mutane masu yawa; wanda kuwa ya bi ni to lalle shi yana tare da ni; wanda kuma ya saɓa mini to lalle Kai Mai gafara ne, Mai jin ƙai."

(37) "Ya Ubangijinmu, lalle ni na zaunar da wasu daga zuriyata a wani kwari wanda ba a shuka a cikinsa(1) kusa da Ɗakinka mai alfarma; ya Ubangijinmu don su tsai da salla, to Ka sanya zukatan mutane su riƙa karkatowa zuwa gare su, kuma Ka arzuta su da 'ya'yan itace don su gode (maka)

(38) "Ya Ubangijinmu, lalle Kai Ka san abin da muke ɓoyewa da abin da muke bayyanawa. Babu wani abu a cikin ƙasa ko a cikin sama da zai ɓuya ga Allah

(39) "Dukkan yabo ya tabbata ga Allah wanda Ya ba ni Isma'ila da Is'haƙa a cikin halin tsufa. Lalle Ubangijina tabbas Mai jin roƙo ne

(40) "Ya Ubangijina, Ka sanya ni in zama mai tsayar da salla da kuma zuriyata. Ya Ubangijinmu, Ka karɓi addu'ata

(41) "Ya Ubangijinmu Ka gafarta mini, ni da iyayena da kuma muminai ranar da hisabi zai kankama."

(42) Kada ka yi tsammanin Allah ba Shi da masaniyar abin da azzalumai suke aikatawa. Yana dai saurara musu ne kawai zuwa ranar da idanuwa za su fito zuru-zuru

(1) Watau kuyangarsa Hajara ( ) da ɗansa Isma'ilu ( ). Ya zaunar da su garin Makka da izinin Allah ( ).

مُهْطِعِينَ مُقْنِعِي رُءُوسِهِمْ لَا يَرْتَدُّ إِلَيْهِمْ طَرْفُهُمْ ۖ
وَأَفْـِٔدَتُهُمْ هَوَآءٌ ﴿٤٣﴾ وَأَنذِرِ ٱلنَّاسَ يَوْمَ يَأْتِيهِمُ ٱلْعَذَابُ
فَيَقُولُ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ رَبَّنَآ أَخِّرْنَآ إِلَىٰٓ أَجَلٍ قَرِيبٍ نُّجِبْ
دَعْوَتَكَ وَنَتَّبِعِ ٱلرُّسُلَ ۗ أَوَلَمْ تَكُونُوٓا۟ أَقْسَمْتُم مِّن قَبْلُ
مَا لَكُم مِّن زَوَالٍ ﴿٤٤﴾ وَسَكَنتُمْ فِى مَسَٰكِنِ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓا۟
أَنفُسَهُمْ وَتَبَيَّنَ لَكُمْ كَيْفَ فَعَلْنَا بِهِمْ وَضَرَبْنَا لَكُمُ
ٱلْأَمْثَالَ ﴿٤٥﴾ وَقَدْ مَكَرُوا۟ مَكْرَهُمْ وَعِندَ ٱللَّهِ مَكْرُهُمْ
وَإِن كَانَ مَكْرُهُمْ لِتَزُولَ مِنْهُ ٱلْجِبَالُ ﴿٤٦﴾ فَلَا
تَحْسَبَنَّ ٱللَّهَ مُخْلِفَ وَعْدِهِۦ رُسُلَهُۥٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ
ذُو ٱنتِقَامٍ ﴿٤٧﴾ يَوْمَ تُبَدَّلُ ٱلْأَرْضُ غَيْرَ ٱلْأَرْضِ وَٱلسَّمَٰوَٰتُ ۖ
وَبَرَزُوا۟ لِلَّهِ ٱلْوَٰحِدِ ٱلْقَهَّارِ ﴿٤٨﴾ وَتَرَى ٱلْمُجْرِمِينَ يَوْمَئِذٍ
مُّقَرَّنِينَ فِى ٱلْأَصْفَادِ ﴿٤٩﴾ سَرَابِيلُهُم مِّن قَطِرَانٍ وَتَغْشَىٰ
وُجُوهَهُمُ ٱلنَّارُ ﴿٥٠﴾ لِيَجْزِىَ ٱللَّهُ كُلَّ نَفْسٍ مَّا كَسَبَتْ ۚ
إِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلْحِسَابِ ﴿٥١﴾ هَٰذَا بَلَٰغٌ لِّلنَّاسِ وَلِيُنذَرُوا۟ بِهِۦ
وَلِيَعْلَمُوٓا۟ أَنَّمَا هُوَ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ وَلِيَذَّكَّرَ أُو۟لُوا۟ ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿٥٢﴾

(43) Suna masu gaggawa masu ɗage da kawunansu sama ba sa ƙiftawa; zukatansu kuma fanko ne (don tsananin firgita)
(44) Kuma ka gargaɗi mutane game da ranar da azaba za ta zo musu, sai waɗanda suka yi kafirci su ce: "Ya Ubangijinmu, Ka saurara mana zuwa ɗan lokaci ƙanƙani, za mu amsa kiranka kuma mu bi manzanni." (Sai a ce da su): "A da ba ku ne kuka yi rantsuwa ba cewa ba za ku gushe ba?
(45) "Kuka kuma zauna a gidajen waɗanda suka zalunci kawunansu, kuma irin yadda Muka yi musu ya bayyana a gare ku, Muka kuma ba ku misalai!"
(46) Haƙiƙa kuma sun shirya makircinsu, sakamakon makircinsu kuma yana wurin Allah, ko da kuwa duwatsu za su gushe don makircinsu
(47) To kada ka yi tsammanin Allah Mai saɓa wa manzanninsa alƙawarinsa ne. Lalle Allah Mabuwayi ne Ma'abocin uƙuba
(48) (Ka tuna) ranar da za a sake ƙasa ba (wannan) ƙasar ba, da kuma sammai (ba waɗannan samman ba. Halittu) kuma suka fito (daga cikin ƙasa) a gaban Allah Makaɗaici, Mai rinjaye
(49) Kuma za ka ga masu laifi a wannan ranar a ƙuƙumce cikin maruruwa
(50) Rigunansu na (tafasasshen) man ƙaɗiran ne[1], kuma wuta za ta lulluɓe fuskokinsu
(51) (An yi musu haka ne) don Allah Ya saka wa kowanne rai da gwargwadon abin da ya aikata. Lalle Allah Mai saurin hisabi ne
(52) Wannan (Alƙur'ani) saƙo ne ga mutane don kuma a gargaɗe su da shi, kuma su san cewa Shi Allah Ɗaya ne, don kuma ma'abota hankali su wa'azantu

(1) Kaɗiran, wani baƙin mai ne kamar kwalta, mai saurin kamawa da wuta, mai kuma ɗan karen wari.

Sura Hijr

سُورَةُ الحِجۡرِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓرۚ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِ وَقُرۡءَانٖ مُّبِينٖ ١ رُّبَمَا يَوَدُّ
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَوۡ كَانُواْ مُسۡلِمِينَ ٢ ذَرۡهُمۡ يَأۡكُلُواْ
وَيَتَمَتَّعُواْ وَيُلۡهِهِمُ ٱلۡأَمَلُۖ فَسَوۡفَ يَعۡلَمُونَ ٣ وَمَآ أَهۡلَكۡنَا
مِن قَرۡيَةٍ إِلَّا وَلَهَا كِتَابٞ مَّعۡلُومٞ ٤ مَّا تَسۡبِقُ مِنۡ أُمَّةٍ
أَجَلَهَا وَمَا يَسۡتَـٔۡخِرُونَ ٥ وَقَالُواْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِي نُزِّلَ عَلَيۡهِ
ٱلذِّكۡرُ إِنَّكَ لَمَجۡنُونٞ ٦ لَّوۡ مَا تَأۡتِينَا بِٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ إِن كُنتَ
مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٧ مَا نُنَزِّلُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَمَا كَانُوٓاْ
إِذٗا مُّنظَرِينَ ٨ إِنَّا نَحۡنُ نَزَّلۡنَا ٱلذِّكۡرَ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ٩
وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ فِي شِيَعِ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٠ وَمَا يَأۡتِيهِم
مِّن رَّسُولٍ إِلَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ١١ كَذَٰلِكَ نَسۡلُكُهُۥ
فِي قُلُوبِ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ١٢ لَا يُؤۡمِنُونَ بِهِۦ وَقَدۡ خَلَتۡ سُنَّةُ ٱلۡأَوَّلِينَ
١٣ وَلَوۡ فَتَحۡنَا عَلَيۡهِم بَابٗا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ فَظَلُّواْ فِيهِ يَعۡرُجُونَ ١٤
لَقَالُوٓاْ إِنَّمَا سُكِّرَتۡ أَبۡصَٰرُنَا بَلۡ نَحۡنُ قَوۡمٞ مَّسۡحُورُونَ ١٥

(1) ALIF LAM RA[1] .
Wadannan ayoyin Littafi ne, kuma abin karatu ne mabayyani
(2) Wadanda suka kafirta za su rika burin ina ma da sun zama Musulmai[2]
(3) Bar su su ci kuma su ji dadi, buri kuma ya shagaltar da su ; sai dai ba da dadewa ba za su sani
(4) Ba wata alkarya da Muka hallakar face tana da wani sanannen lokaci (a wurin Allah)
(5) Ba wata al'umma da za ta riga lokacin da aka iyakance mata ko su jinkirta bayansa
(6) Suka kuma ce: "Ya kai wanda aka saukar wa da Alkur'ani, lalle kai tabbas mahaukaci ne
(7) "Me zai hana ka zo mana da mala'iku idan kana daga cikin masu gaskiya?"
(8) (Allah ya ce): "Ba ma saukar da mala'iku sai da gaskiya[3]; inda kuwa haka ya faru, to ba za a saurara musu ba."
(9) Lalle Mu Muka saukar da Alkur'ani, lalle kuma tabbas Mu za Mu kiyaye shi
(10) Hakika kuma Mun aiko (manzanni) a gabaninka cikin al'ummun farko
(11) Ba kuwa wani manzo da zai zo musu sai sun zamanto suna yi masa izgili
(12) Kamar haka ne Muke shigar da shi cikin zukatan kafirai
(13) Ba za su yi imani da shi ba; hakika kuma hanyar (sakamakon) mutanen farko ta gabata (wato hallakarwa)
(14) Idan da Mun bude musu kofar sama har suka dinga hawa ta cikinta
(15) Tabbas da sun ce: "Ai an yi mana rufa-ido ne kawai; a'a, kai mu dai mutane ne da aka sihirce."

(1) Duba Suratul Bakara, aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Watau a ranar alkiyama ko kuma lokacin mutuwarsa.

(3) Watau sai idan lokacin da za a hallaka su ya zo.

وَلَقَدْ جَعَلْنَا فِي ٱلسَّمَآءِ بُرُوجًا وَزَيَّنَّٰهَا لِلنَّٰظِرِينَ ﴿١٦﴾
وَحَفِظْنَٰهَا مِن كُلِّ شَيْطَٰنٍ رَّجِيمٍ ﴿١٧﴾ إِلَّا مَنِ ٱسْتَرَقَ ٱلسَّمْعَ
فَأَتْبَعَهُۥ شِهَابٌ مُّبِينٌ ﴿١٨﴾ وَٱلْأَرْضَ مَدَدْنَٰهَا وَأَلْقَيْنَا فِيهَا
رَوَٰسِيَ وَأَنۢبَتْنَا فِيهَا مِن كُلِّ شَيْءٍ مَّوْزُونٍ ﴿١٩﴾ وَجَعَلْنَا لَكُمْ
فِيهَا مَعَٰيِشَ وَمَن لَّسْتُمْ لَهُۥ بِرَٰزِقِينَ ﴿٢٠﴾ وَإِن مِّن شَيْءٍ إِلَّا
عِندَنَا خَزَآئِنُهُۥ وَمَا نُنَزِّلُهُۥٓ إِلَّا بِقَدَرٍ مَّعْلُومٍ ﴿٢١﴾ وَأَرْسَلْنَا
ٱلرِّيَٰحَ لَوَٰقِحَ فَأَنزَلْنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَسْقَيْنَٰكُمُوهُ وَمَآ أَنتُمْ
لَهُۥ بِخَٰزِنِينَ ﴿٢٢﴾ وَإِنَّا لَنَحْنُ نُحْيِۦ وَنُمِيتُ وَنَحْنُ ٱلْوَٰرِثُونَ ﴿٢٣﴾
وَلَقَدْ عَلِمْنَا ٱلْمُسْتَقْدِمِينَ مِنكُمْ وَلَقَدْ عَلِمْنَا ٱلْمُسْتَـْٔخِرِينَ
﴿٢٤﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ هُوَ يَحْشُرُهُمْ ۚ إِنَّهُۥ حَكِيمٌ عَلِيمٌ ﴿٢٥﴾ وَلَقَدْ خَلَقْنَا
ٱلْإِنسَٰنَ مِن صَلْصَٰلٍ مِّنْ حَمَإٍ مَّسْنُونٍ ﴿٢٦﴾ وَٱلْجَآنَّ خَلَقْنَٰهُ مِن
قَبْلُ مِن نَّارِ ٱلسَّمُومِ ﴿٢٧﴾ وَإِذْ قَالَ رَبُّكَ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ إِنِّي خَٰلِقٌۢ بَشَرًا
مِّن صَلْصَٰلٍ مِّنْ حَمَإٍ مَّسْنُونٍ ﴿٢٨﴾ فَإِذَا سَوَّيْتُهُۥ وَنَفَخْتُ فِيهِ
مِن رُّوحِي فَقَعُوا۟ لَهُۥ سَٰجِدِينَ ﴿٢٩﴾ فَسَجَدَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ كُلُّهُمْ
أَجْمَعُونَ ﴿٣٠﴾ إِلَّآ إِبْلِيسَ أَبَىٰٓ أَن يَكُونَ مَعَ ٱلسَّٰجِدِينَ ﴿٣١﴾

(16) Hakika kuma Mun sanya taurari a sama, Muka kuma kawata ta ga masu gani
(17) Kuma Muka kiyaye ta daga duk wani shaidani la'ananne
(18) Sai dai wanda ya yi satar sauraro, sannan sai tauraro mai harshen wuta ya biyo shi
(19) Kasa kuma Mun shimfida ta Muka sanya manyan duwatsu a cikinta, Muka kuma tsiro da kowane abu a cikinta kayyadajje
(20) Muka kuma sanya muku kayan rayuwa a cikinta, da kuma wanda ba ku ne kuke arzuta shi ba (wato bayi da dabbobi)
(21) Babu wani abu wanda taskokinsa ba a wurinmu suke ba, kuma ba ma saukar da shi sai daidai wani gwargwado sananne
(22) Muka kuma aiko da iska mai yin barbara (ga giza-gizai), sai Muka saukar da ruwa daga sama Muka shayar da ku da shi, ba kuma ku ne masu taskance shi ba
(23) Lalle kuma tabbas Mu Muke rayawa kuma Muke kashewa, Mu ne kuma Masu gaje (komai)
(24) Hakika kuma Mun san marigaya daga cikinku kuma hakika Mun san masu biyowa baya(1)
(25) Lalle Ubangijinka kuma Shi zai tattara su. Lalle shi Mai hikima ne, Masani
(26) Kuma hakika Mun halicci mutum daga busasshen tabo mai amo na wani yumbu mai wari
(27) Aljani kuwa Mun halicce shi ne gabanin (halittar mutum) daga wuta mai tsananin zafi
(28) Kuma (ka tuna) lokacin da Ubangijinka ya ce da mala'iku: "Lalle Ni zan halicci mutum daga busasshen tabo mai amo na wani yumbu mai wari
(29) "To idan Na daidaita shi Na kuma busa masa daga ruhina, to ku fadi kuna masu sujjada a gare shi."
(30) Sai mala'iku dukkaninsu suka yi sujjada gaba daya
(31) Sai Iblis ya ki ya kasance tare da masu yin sujjadar

(1) Watau Allah ( ) ya san wadanda za a riga haihuwarsu su riga mutuwa, ya san kuma wadanda za a haife su, daga baya su mutu.

قَالَ يَٰٓإِبۡلِيسُ مَا لَكَ أَلَّا تَكُونَ مَعَ ٱلسَّٰجِدِينَ ﴿٣٢﴾ قَالَ لَمۡ أَكُن
لِّأَسۡجُدَ لِبَشَرٍ خَلَقۡتَهُۥ مِن صَلۡصَٰلٖ مِّنۡ حَمَإٖ مَّسۡنُونٖ ﴿٣٣﴾
قَالَ فَٱخۡرُجۡ مِنۡهَا فَإِنَّكَ رَجِيمٞ ﴿٣٤﴾ وَإِنَّ عَلَيۡكَ ٱللَّعۡنَةَ إِلَىٰ يَوۡمِ
ٱلدِّينِ ﴿٣٥﴾ قَالَ رَبِّ فَأَنظِرۡنِيٓ إِلَىٰ يَوۡمِ يُبۡعَثُونَ ﴿٣٦﴾ قَالَ فَإِنَّكَ
مِنَ ٱلۡمُنظَرِينَ ﴿٣٧﴾ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡوَقۡتِ ٱلۡمَعۡلُومِ ﴿٣٨﴾ قَالَ رَبِّ بِمَآ
أَغۡوَيۡتَنِي لَأُزَيِّنَنَّ لَهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَأُغۡوِيَنَّهُمۡ أَجۡمَعِينَ
﴿٣٩﴾ إِلَّا عِبَادَكَ مِنۡهُمُ ٱلۡمُخۡلَصِينَ ﴿٤٠﴾ قَالَ هَٰذَا صِرَٰطٌ عَلَيَّ
مُسۡتَقِيمٌ ﴿٤١﴾ إِنَّ عِبَادِي لَيۡسَ لَكَ عَلَيۡهِمۡ سُلۡطَٰنٌ إِلَّا مَنِ
ٱتَّبَعَكَ مِنَ ٱلۡغَاوِينَ ﴿٤٢﴾ وَإِنَّ جَهَنَّمَ لَمَوۡعِدُهُمۡ أَجۡمَعِينَ ﴿٤٣﴾
لَهَا سَبۡعَةُ أَبۡوَٰبٖ لِّكُلِّ بَابٖ مِّنۡهُمۡ جُزۡءٞ مَّقۡسُومٌ ﴿٤٤﴾ إِنَّ
ٱلۡمُتَّقِينَ فِي جَنَّٰتٖ وَعُيُونٍ ﴿٤٥﴾ ٱدۡخُلُوهَا بِسَلَٰمٍ ءَامِنِينَ ﴿٤٦﴾
وَنَزَعۡنَا مَا فِي صُدُورِهِم مِّنۡ غِلٍّ إِخۡوَٰنًا عَلَىٰ سُرُرٖ مُّتَقَٰبِلِينَ
﴿٤٧﴾ لَا يَمَسُّهُمۡ فِيهَا نَصَبٞ وَمَا هُم مِّنۡهَا بِمُخۡرَجِينَ ﴿٤٨﴾
نَبِّئۡ عِبَادِيٓ أَنِّيٓ أَنَا ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٤٩﴾ وَأَنَّ عَذَابِي
هُوَ ٱلۡعَذَابُ ٱلۡأَلِيمُ ﴿٥٠﴾ وَنَبِّئۡهُمۡ عَن ضَيۡفِ إِبۡرَٰهِيمَ ﴿٥١﴾

(32) ا(Allah) Ya ce: “Ya Iblis, me ka taka da ba za ka kasance tare da masu sujjada ba?”
(33) (Iblis) ya ce: “Ba zai yiwu ba ni in yi sujjada ga wani mutum wanda Ka halitta daga busasshen tabo mai amo na wani yumbu mai wari.”
(34) (Allah) Ya ce: “To ka fita daga cikinta (Aljannar), lalle kai korarre ne (daga rahamar Allah)
(35) “Lalle kuma la’ana ta tabbata a kanka har zuwa ranar alkiyama.”
(36) (Iblis) ya ce: “Ya Ubangijina Ka saurara min har zuwa ranar da za a tashe su (watau matattu).”
(37) (Allah) Ya ce: “To lalle kana daga cikin waɗanda za a saurar musu(38)“Har zuwa rana mai sanannen lokaci.”
(39) (Iblis) ya ce: “Ubangijina, saboda ɓatar da ni da Ka yi, to lalle kuwa zan ƙawata musu (ɓarna) a bayan ƙasa, kuma tabbas zan ɓatar da su baki ɗaya
(40) “Sai fa bayinka zaɓaɓɓu daga cikinsu.”
(41) (Allah) Ya ce: “Wannan hanya ce madaidaiciya, mai kaiwa gare Ni
(42) “Lalle bayina ba ka da wani iko a kansu, sai dai wanda ya bi ka daga ɓatattu
(43) “Lalle kuma Jahannama tabbas makomarsu ce baki ɗaya
(44) “Tana da ƙofofi bakwai, kowacce ƙofa tana da wani kaso (na kafirai) sananne (da za su shiga ta nan).”
(45) Lalle masu kiyaye dokokin Allah suna cikin gidajen Aljanna da idanuwan (ruwa)
(46) (A ce da su): “Ku shige ta lafiya lau kuna amintattu.”
(47) Muka kuma cire abin da ke cikin zukatansu na ƙullata (suka zama) ‘yan’uwa a kan gadaje suna fuskantar juna
(48) Wata gajiya ba za ta shafe su ba, kuma su ba waɗanda za a fitar ba ne
(49) Ka bai wa bayina labarin cewa lalle Ni, Ni ne Mai gafara, Mai jin ƙaiu
(50) Kuma lalle azabata ita ce azaba mai raɗaɗi
(51) Kuma ka ba su labari game da baƙin Ibrahimu[1]

(1) Su ne mala’ikun da suka ziyarci Ibrahim ( ) a kan hanyarsu ta zuwa hallaka mutanen Annabi Luɗu ( ).

إِذْ دَخَلُوا۟ عَلَيْهِ فَقَالُوا۟ سَلَٰمًا ۖ قَالَ إِنَّا مِنكُمْ وَجِلُونَ ﴿٥٢﴾ قَالُوا۟
لَا تَوْجَلْ إِنَّا نُبَشِّرُكَ بِغُلَٰمٍ عَلِيمٍ ﴿٥٣﴾ قَالَ أَبَشَّرْتُمُونِى عَلَىٰٓ أَن
مَّسَّنِىَ ٱلْكِبَرُ فَبِمَ تُبَشِّرُونَ ﴿٥٤﴾ قَالُوا۟ بَشَّرْنَٰكَ بِٱلْحَقِّ
فَلَا تَكُن مِّنَ ٱلْقَٰنِطِينَ ﴿٥٥﴾ قَالَ وَمَن يَقْنَطُ مِن رَّحْمَةِ
رَبِّهِۦٓ إِلَّا ٱلضَّآلُّونَ ﴿٥٦﴾ قَالَ فَمَا خَطْبُكُمْ أَيُّهَا ٱلْمُرْسَلُونَ
﴿٥٧﴾ قَالُوٓا۟ إِنَّآ أُرْسِلْنَآ إِلَىٰ قَوْمٍ مُّجْرِمِينَ ﴿٥٨﴾ إِلَّآ ءَالَ لُوطٍ
إِنَّا لَمُنَجُّوهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٥٩﴾ إِلَّا ٱمْرَأَتَهُۥ قَدَّرْنَآ إِنَّهَا لَمِنَ
ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿٦٠﴾ فَلَمَّا جَآءَ ءَالَ لُوطٍ ٱلْمُرْسَلُونَ ﴿٦١﴾ قَالَ
إِنَّكُمْ قَوْمٌ مُّنكَرُونَ ﴿٦٢﴾ قَالُوا۟ بَلْ جِئْنَٰكَ بِمَا كَانُوا۟ فِيهِ
يَمْتَرُونَ ﴿٦٣﴾ وَأَتَيْنَٰكَ بِٱلْحَقِّ وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَ ﴿٦٤﴾ فَأَسْرِ
بِأَهْلِكَ بِقِطْعٍ مِّنَ ٱلَّيْلِ وَٱتَّبِعْ أَدْبَٰرَهُمْ وَلَا يَلْتَفِتْ مِنكُمْ أَحَدٌ
وَٱمْضُوا۟ حَيْثُ تُؤْمَرُونَ ﴿٦٥﴾ وَقَضَيْنَآ إِلَيْهِ ذَٰلِكَ ٱلْأَمْرَ أَنَّ
دَابِرَ هَٰٓؤُلَآءِ مَقْطُوعٌ مُّصْبِحِينَ ﴿٦٦﴾ وَجَآءَ أَهْلُ ٱلْمَدِينَةِ
يَسْتَبْشِرُونَ ﴿٦٧﴾ قَالَ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ ضَيْفِى فَلَا تَفْضَحُونِ ﴿٦٨﴾
وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَلَا تُخْزُونِ ﴿٦٩﴾ قَالُوٓا۟ أَوَلَمْ نَنْهَكَ عَنِ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٧٠﴾

(52) Lokacin da suka shiga wurinsa suka ce: “Muna yi maka sallama”, ya ce: “Lalle mu a tsorace muke da ku.”
(53) Suka ce: “Kada ka ji tsoro, lalle mu muna yi maka albishir ne da (samun) yaro mai ilimi.”
(54) Ya ce: “Yanzu kwa yi mini albishir bayan kuwa ga shi tsufa ya kama ni? To da me kuma za ku yi min albishir?!”
(55) Suka ce: “Mun yi maka albishir da gaskiya ne, don haka kada ka zamo daga masu ɗebe ƙauna.”
(56) Ya ce: “Ba wanda zai ɗebe ƙauna daga rahamar Ubangijinsa, sai ɓatattun (mutane).”
(57) Ya ce: “Me yake tafe da ku ya ku waɗannan manzanni?”
(58) Suka ce: “Lalle mu an aike mu ne zuwa ga wasu mutane masu laifi (wato mutanen Luɗu)
(59) “In ban da iyalin Luɗu, lalle tabbas za mu tserar da su baki ɗaya
(60) “Sai fa matarsa ita kam mun ƙaddara cewa tabbas za ta zama cikin halakakku.”
(61) To lokacin da manzannin suka zo wa iyalin Luɗu
(62) Ya ce: “Lalle ku wasu mutane ne da ba a san su ba.”
(63) Suka ce: “A’a, mu mun zo maka ne da abin da (mutanenka) suke kokwanto game da shi
(64) “Mun kuma zo maka da dahir, lalle kuma tabbas mu masu gaskiya ne
(65) “Sai ka tafi da iyalinka cikin wani yankin dare ka kuma riƙa bin su a baya, kada kuwa ɗaya daga cikinku ya waiwaya, kuma ku tafi inda aka umarce ku.”
(66) Muka kuwa sanar da shi abin da Muka ƙaddara na wannan al’amari cewa, ƙarshen waɗannan zai yanke ne da asuba
(67) Mutanen garin kuma suka zo suna murna (da ganin baƙin)
(68) Ya ce: “Lalle waɗannan baƙina ne, kada fa ku kunyata ni
(69) “Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kada ku tozarta ni[1].”
(70) Suka ce: “Ashe ba mu hana ka (ka saukar da) mutane (baƙi ba)?”

(1) Annabi Luɗu ya yi wannan maganar ne kafin ya san cewa waɗannan baƙi nasa mala’iku ne.

قَالَ هَٰٓؤُلَآءِ بَنَاتِيٓ إِن كُنتُمۡ فَٰعِلِينَ ٧١ لَعَمۡرُكَ إِنَّهُمۡ لَفِي سَكۡرَتِهِمۡ
يَعۡمَهُونَ ٧٢ فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلصَّيۡحَةُ مُشۡرِقِينَ ٧٣ فَجَعَلۡنَا عَٰلِيَهَا
سَافِلَهَا وَأَمۡطَرۡنَا عَلَيۡهِمۡ حِجَارَةٗ مِّن سِجِّيلٍ ٧٤ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَأٓيَٰتٖ لِّلۡمُتَوَسِّمِينَ ٧٥ وَإِنَّهَا لَبِسَبِيلٖ مُّقِيمٍ ٧٦ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَأٓيَةٗ لِّلۡمُؤۡمِنِينَ ٧٧ وَإِن كَانَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡأَيۡكَةِ لَظَٰلِمِينَ ٧٨
فَٱنتَقَمۡنَا مِنۡهُمۡ وَإِنَّهُمَا لَبِإِمَامٖ مُّبِينٖ ٧٩ وَلَقَدۡ كَذَّبَ أَصۡحَٰبُ
ٱلۡحِجۡرِ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ٨٠ وَءَاتَيۡنَٰهُمۡ ءَايَٰتِنَا فَكَانُواْ عَنۡهَا مُعۡرِضِينَ
٨١ وَكَانُواْ يَنۡحِتُونَ مِنَ ٱلۡجِبَالِ بُيُوتًا ءَامِنِينَ ٨٢ فَأَخَذَتۡهُمُ
ٱلصَّيۡحَةُ مُصۡبِحِينَ ٨٣ فَمَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٨٤
وَمَا خَلَقۡنَا ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَآ إِلَّا بِٱلۡحَقِّۗ وَإِنَّ
ٱلسَّاعَةَ لَأٓتِيَةٞۖ فَٱصۡفَحِ ٱلصَّفۡحَ ٱلۡجَمِيلَ ٨٥ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ
ٱلۡخَلَّٰقُ ٱلۡعَلِيمُ ٨٦ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَٰكَ سَبۡعٗا مِّنَ ٱلۡمَثَانِي
وَٱلۡقُرۡءَانَ ٱلۡعَظِيمَ ٨٧ لَا تَمُدَّنَّ عَيۡنَيۡكَ إِلَىٰ مَا مَتَّعۡنَا بِهِۦٓ أَزۡوَٰجٗا
مِّنۡهُمۡ وَلَا تَحۡزَنۡ عَلَيۡهِمۡ وَٱخۡفِضۡ جَنَاحَكَ لِلۡمُؤۡمِنِينَ ٨٨ وَقُلۡ
إِنِّيٓ أَنَا ٱلنَّذِيرُ ٱلۡمُبِينُ ٨٩ كَمَآ أَنزَلۡنَا عَلَى ٱلۡمُقۡتَسِمِينَ ٩٠

(71) Ya ce: “Ga ‘ya’yana nan (ku aura)[1] idan kun kasance masu aikata (haka)
(72) “Na rantse da rayuwarka lalle su tabbas suna cikin mayensu suna ta ɗimuwa.”
(73) Sai tsawa ta auka musu lokacin hudowar rana
(74) Sai Muka mayar da samanta ya koma ƙasa, Muka kuma yi musu ruwan duwatsu soyayyu
(75) Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga masu hangen nesa
(76) Lalle kuma ita (alƙaryar) tabbas tana kan wani gwadabe ne miƙaƙƙe
(77) Lalle a game da wannan tabbas akwai izina ga muminai
(78) Lalle kuma mutanen (alƙaryar) Mai duhuwa tabbas sun zamanto azzalumai
(79) Sai Muka azabtar da su, lalle kuma su biyun suna kan wani gwadabe ne fitacce
(80) Haƙiƙa kuma mutanen Hijiru (Samudawa) sun ƙaryata manzanni
(81) Muka kuma kawo musu ayoyinmu, sai suka zamanto masu bijirewa daga gare su
(82) Sun zamanto suna fafe duwatsu suna yin gidaje su zama cikin aminci
(83) Sai tsawa ta auka musu da asuba
(84) Sai abin da suka zamanto suna aikatawa bai amfane su ba
(85) Ba Mu kuma halicci sammai da ƙasa ba sai da gaskiya. Kuma lalle alƙiyama tabbas mai zuwa ce, sai ka yi afuwa kyakkyawar afuwa[2]
(86) Hakika Mola wako Mlezi ndiye Muumbaji (wa kila kitu tena) Mjuzi sana
(87) Na tumekupa Aya saba (za Sura Al-fatiha) zisomwazo mara kwa mara, na Kur’ani Tukufu
(88) Usiɓikodolee macho yako ɓitu tuliɓyo waneemesha makundi fulani kati yao (hao makafiri), wala usiwahuzunikie (wasipoamaini). Na wainamishie bawa lako (la huruma) Waumini
(89) Na sema: Hakika mimi ni muonyaji mwenye kubainisha
(90) (Tumekuteremshia hii Kur’an) Kama tuliɓyowateremshia (Kitabu Mayahudi na Manaswara) walikigawanya (kwa kuamini baadhi na kukataa baadhi)inisha

(1) Yana nufin matan al’ummarsa.

(2) Watau afuwar da babu cutarwa a cikinta sai dai kyautatawa ga wanda ya munana.

الَّذِينَ جَعَلُوا الْقُرْآنَ عِضِينَ ﴿٩١﴾ فَوَرَبِّكَ لَنَسْأَلَنَّهُمْ
أَجْمَعِينَ ﴿٩٢﴾ عَمَّا كَانُوا يَعْمَلُونَ ﴿٩٣﴾ فَاصْدَعْ بِمَا تُؤْمَرُ وَأَعْرِضْ
عَنِ الْمُشْرِكِينَ ﴿٩٤﴾ إِنَّا كَفَيْنَاكَ الْمُسْتَهْزِئِينَ ﴿٩٥﴾ الَّذِينَ
يَجْعَلُونَ مَعَ اللَّهِ إِلَٰهًا آخَرَ ۚ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ﴿٩٦﴾ وَلَقَدْ نَعْلَمُ
أَنَّكَ يَضِيقُ صَدْرُكَ بِمَا يَقُولُونَ ﴿٩٧﴾ فَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ وَكُنْ
مِنَ السَّاجِدِينَ ﴿٩٨﴾ وَاعْبُدْ رَبَّكَ حَتَّىٰ يَأْتِيَكَ الْيَقِينُ ﴿٩٩﴾

سُورَةُ النَّحْلِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

أَتَىٰ أَمْرُ اللَّهِ فَلَا تَسْتَعْجِلُوهُ ۚ سُبْحَانَهُ وَتَعَالَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ
﴿١﴾ يُنَزِّلُ الْمَلَائِكَةَ بِالرُّوحِ مِنْ أَمْرِهِ عَلَىٰ مَنْ يَشَاءُ مِنْ
عِبَادِهِ أَنْ أَنْذِرُوا أَنَّهُ لَا إِلَٰهَ إِلَّا أَنَا فَاتَّقُونِ ﴿٢﴾ خَلَقَ
السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضَ بِالْحَقِّ ۚ تَعَالَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٣﴾ خَلَقَ
الْإِنْسَانَ مِنْ نُطْفَةٍ فَإِذَا هُوَ خَصِيمٌ مُبِينٌ ﴿٤﴾ وَالْأَنْعَامَ
خَلَقَهَا ۗ لَكُمْ فِيهَا دِفْءٌ وَمَنَافِعُ وَمِنْهَا تَأْكُلُونَ
﴿٥﴾ وَلَكُمْ فِيهَا جَمَالٌ حِينَ تُرِيحُونَ وَحِينَ تَسْرَحُونَ ﴿٦﴾

(91) (Su ne) waɗanda suka mai da Alkur'ani kashi-kashi[1]
(92) (Na rantse) da Ubangijinka tabbas za Mu tambaye su gaba ɗaya
(93) Game da abin da suka kasance suna aikatawa
(94) To ka tsage gaskiyar abin da aka umarce ka da shi, ka kuma kawar da kanka daga mushirikai
(95) Lalle Mu Mun isar maka (sharrin) masu izgili
(96) (Su ne) waɗanda suke sanya wani abin bauta tare da Allah. Ba ko da daɗewa ba za su sani
(97) Haƙiƙa kuma Muna sane da cewa ƙirjinka yana ƙunci game da abin da suke faɗa
(98) To sai ka yi tasbihi tare da godiyar Ubangijinka, ka kuma zamo cikin masu sujjada
(99) Ka kuma bauta wa Ubangijinka har yaƙini ya zo maka (wato mutuwa)

Sura Nahl

(1) Al'amarin Allah ya zo, don haka kada ku nemi gaggauto shi (watau ranar alƙiyama). Tsarki ya tabbata a gare Shi, Ya kuma ɗaukaka daga abin da suke tara (Shi da shi)
(2) Yana saukar da mala'iku da wahayi na umarninsa ga waɗanda Ya ga dama daga bayinsa da cewa,: "Ku yi gargaɗi cewa,, lalle ba wani abin bauta sai Ni, to sai ku kiyaye dokokina."
(3) Ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya. Ya ɗaukaka daga abin da suke tara (Shi da shi)
(4) Ya halicci mutum daga maniyyi, sai ga shi mai jayayya a fili
(5) Ya kuma halicci dabbobin ni'ima. Kuna da (abin) ɗumama jiki tattare da su, da kuma sauran abubuwan amfani; daga gare su ne kuma kuke ci
(6) Kuma kuna da abubuwan ado a tattare da su, lokacin da kuke dawowa (daga kiwo) da kuma lokacin da kuke fita (da safe)

(1) Watau suka yi imani da wani ɓangare suka kafirce wa wani ɓangare.

وَتَحْمِلُ أَثْقَالَكُمْ إِلَىٰ بَلَدٍ لَّمْ تَكُونُوا۟ بَٰلِغِيهِ إِلَّا بِشِقِّ
ٱلْأَنفُسِ ۚ إِنَّ رَبَّكُمْ لَرَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿٧﴾ وَٱلْخَيْلَ وَٱلْبِغَالَ
وَٱلْحَمِيرَ لِتَرْكَبُوهَا وَزِينَةً ۚ وَيَخْلُقُ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿٨﴾
وَعَلَى ٱللَّهِ قَصْدُ ٱلسَّبِيلِ وَمِنْهَا جَآئِرٌ ۚ وَلَوْ شَآءَ لَهَدَىٰكُمْ
أَجْمَعِينَ ﴿٩﴾ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً لَّكُم
مِّنْهُ شَرَابٌ وَمِنْهُ شَجَرٌ فِيهِ تُسِيمُونَ ﴿١٠﴾ يُنۢبِتُ لَكُم
بِهِ ٱلزَّرْعَ وَٱلزَّيْتُونَ وَٱلنَّخِيلَ وَٱلْأَعْنَٰبَ وَمِن كُلِّ
ٱلثَّمَرَٰتِ ۗ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً لِّقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ
﴿١١﴾ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ وَٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ ۖ
وَٱلنُّجُومُ مُسَخَّرَٰتٌۢ بِأَمْرِهِۦٓ ۗ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ
يَعْقِلُونَ ﴿١٢﴾ وَمَا ذَرَأَ لَكُمْ فِى ٱلْأَرْضِ مُخْتَلِفًا
أَلْوَٰنُهُۥ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً لِّقَوْمٍ يَذَّكَّرُونَ ﴿١٣﴾
وَهُوَ ٱلَّذِى سَخَّرَ ٱلْبَحْرَ لِتَأْكُلُوا۟ مِنْهُ لَحْمًا طَرِيًّا
وَتَسْتَخْرِجُوا۟ مِنْهُ حِلْيَةً تَلْبَسُونَهَا ۖ وَتَرَى ٱلْفُلْكَ مَوَاخِرَ
فِيهِ وَلِتَبْتَغُوا۟ مِن فَضْلِهِۦ وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿١٤﴾

(7) Suna kuma ɗaukar kayayyakinku masu nauyi zuwa garin da ba za ku iya isar sa ba sai da ƙyar. Lalle Ubangijinku tabbas Mai tausayi ne, Mai rahama
(8) Dawakai da kuma alfadarai da jakai (Ya halitta muku su) don ku hau su kuma su zama ado. Zai kuma hallici abin da ma ba ku sani ba
(9) Kuma bayanin hanya madaidaiciya haƙƙi ne a kan Allah, daga kuma (hanyar) akwai karkatacciya. Da kuma Ya ga dama lalle da Ya shirye ku gaba ɗaya
(10) Shi ne wanda Ya saukar da ruwa daga sama; daga gare shi ne kuke sha, daga gare shi ne kuma bishiyoyi suke (sha) wanda da su ne kuke kiwon (dabbobinku)
(11) Da shi (ruwan) Yake tsiro muku da shuke-shuke da zaitun da dabinai da inabai da kuma kowanne irin 'ya'yan itace. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya ga mutanen da suke tunani
(12) Ya kuma hore muku dare da rana da kuma wata; taurari ma ababen horewa ne da umarninsa. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutane masu hankali
(13) Da kuma abubuwan da Ya halitta muku a ƙasa masu launi iri daban-daban. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya ga mutanen da suke wa'azantuwa
14) Shi ne kuma wanda Ya hore muku kogi don ku ci daddaɗan nama mai taushi daga gare shi, ku kuma riƙa fito da kayan ado daga cikinsa waɗanda kuke ɗaurawa, kuma ka ga jiragen ruwa suna keta shi don kuma ku nema daga falalarsa (Ubangiji) don kuma ku riƙa godiya

وَأَلْقَىٰ فِي ٱلْأَرْضِ رَوَٰسِيَ أَن تَمِيدَ بِكُمْ وَأَنْهَٰرًا وَسُبُلًا
لَّعَلَّكُمْ تَهْتَدُونَ ﴿١٥﴾ وَعَلَٰمَٰتٍ ۚ وَبِٱلنَّجْمِ هُمْ يَهْتَدُونَ
﴿١٦﴾ أَفَمَن يَخْلُقُ كَمَن لَّا يَخْلُقُ ۗ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ﴿١٧﴾ وَإِن
تَعُدُّوا۟ نِعْمَةَ ٱللَّهِ لَا تُحْصُوهَآ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٨﴾
وَٱللَّهُ يَعْلَمُ مَا تُسِرُّونَ وَمَا تُعْلِنُونَ ﴿١٩﴾ وَٱلَّذِينَ يَدْعُونَ
مِن دُونِ ٱللَّهِ لَا يَخْلُقُونَ شَيْـًٔا وَهُمْ يُخْلَقُونَ ﴿٢٠﴾ أَمْوَٰتٌ
غَيْرُ أَحْيَآءٍ ۖ وَمَا يَشْعُرُونَ أَيَّانَ يُبْعَثُونَ ﴿٢١﴾ إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ
وَٰحِدٌ ۚ فَٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِٱلْءَاخِرَةِ قُلُوبُهُم مُّنكِرَةٌ وَهُم
مُّسْتَكْبِرُونَ ﴿٢٢﴾ لَا جَرَمَ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا
يُعْلِنُونَ ۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلْمُسْتَكْبِرِينَ ﴿٢٣﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُم
مَّاذَآ أَنزَلَ رَبُّكُمْ قَالُوٓا۟ أَسَٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٢٤﴾ لِيَحْمِلُوٓا۟
أَوْزَارَهُمْ كَامِلَةً يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۙ وَمِنْ أَوْزَارِ ٱلَّذِينَ يُضِلُّونَهُم
بِغَيْرِ عِلْمٍ ۗ أَلَا سَآءَ مَا يَزِرُونَ ﴿٢٥﴾ قَدْ مَكَرَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ
فَأَتَى ٱللَّهُ بُنْيَٰنَهُم مِّنَ ٱلْقَوَاعِدِ فَخَرَّ عَلَيْهِمُ ٱلسَّقْفُ
مِن فَوْقِهِمْ وَأَتَىٰهُمُ ٱلْعَذَابُ مِنْ حَيْثُ لَا يَشْعُرُونَ ﴿٢٦﴾

(15) Ya kuma sanya wa ƙasa turaku don kada ta rika tangal-tangal da ku da kuma ƙoramu da hanyoyi don ku rika gane (inda kuka dosa)
(16) Da kuma alamomin (hanya). Da kuma taurari ne suke gane (inda suka dosa)
(17) Yanzu wanda Yake halitta (zai yi) daidai da wanda ba ya halitta? Yanzo ba kwa wa'a zantu ba?
(18) Idan kuma da za ku ƙirga ni'imar Allah to ba za ku iya ƙididdige ta ba. Lalle Allah tabbas Mai gafara ne, Mai jin ƙai
(19) Allah kuma Ya san abin da kuke ɓoyewa da abin da kuke bayyanawa
(20) Waɗannan kuma suke bauta wa ba Allah ba, ba sa iya halittar komai, su ne ma ake halittar su
(21) Matattu ne su ba rayayyu ba; ba sa kuma sanin sanda za a tashe su
(22) Abin bautarku Abin bauta ne Ɗaya, sai dai waɗanda ba sa yin imani da ranar lahira zukatansu masu musun hakan ne, kuma su masu girman kai ne
(23) Ba shakka, lalle Allah Yana sane da abin da suke ɓoyewa da abin da suke bayyanawa. Lalle Shi ba Ya son masu girman kai
(24) Idan kuma aka ce da su: "Me Ubangijinku Ya saukar?" (Sai) su ce: "Tatsuniyoyin mutanen farko."
(25) (Wannan kuwa) don su ɗauki laifukansu cikakku ranar alƙiyama, da kuma laifukan waɗanda suke ɓatarwa ba da ilimi ba. Ku saurara, abin da suke ɗauka ya munana!
(26) Haƙiƙa waɗanda suka gabace su sun shirya makirci, sai Allah Ya tumɓuke gininsu daga harsashi, sai rufin ya rifto a kansu daga samansu, azaba kuma ta zo musu ta inda ba sa tsammani

ثُمَّ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يُخْزِيهِمْ وَيَقُولُ أَيْنَ شُرَكَآءِىَ ٱلَّذِينَ
كُنتُمْ تُشَٰٓقُّونَ فِيهِمْ ۚ قَالَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْعِلْمَ إِنَّ ٱلْخِزْىَ
ٱلْيَوْمَ وَٱلسُّوٓءَ عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٧﴾ ٱلَّذِينَ تَتَوَفَّىٰهُمُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ
ظَالِمِىٓ أَنفُسِهِمْ ۖ فَأَلْقَوُا۟ ٱلسَّلَمَ مَا كُنَّا نَعْمَلُ مِن سُوٓءٍ ۚ بَلَىٰٓ
إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٢٨﴾ فَٱدْخُلُوٓا۟ أَبْوَٰبَ جَهَنَّمَ
خَٰلِدِينَ فِيهَا ۖ فَلَبِئْسَ مَثْوًى ٱلْمُتَكَبِّرِينَ ﴿٢٩﴾ ۞ وَقِيلَ
لِلَّذِينَ ٱتَّقَوْا۟ مَاذَآ أَنزَلَ رَبُّكُمْ ۚ قَالُوا۟ خَيْرًا ۗ لِّلَّذِينَ أَحْسَنُوا۟ فِى
هَٰذِهِ ٱلدُّنْيَا حَسَنَةٌ ۚ وَلَدَارُ ٱلْءَاخِرَةِ خَيْرٌ ۚ وَلَنِعْمَ دَارُ ٱلْمُتَّقِينَ
﴿٣٠﴾ جَنَّٰتُ عَدْنٍ يَدْخُلُونَهَا تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ
لَهُمْ فِيهَا مَا يَشَآءُونَ ۚ كَذَٰلِكَ يَجْزِى ٱللَّهُ ٱلْمُتَّقِينَ ﴿٣١﴾
ٱلَّذِينَ تَتَوَفَّىٰهُمُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ طَيِّبِينَ ۙ يَقُولُونَ سَلَٰمٌ عَلَيْكُمُ
ٱدْخُلُوا۟ ٱلْجَنَّةَ بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٣٢﴾ هَلْ يَنظُرُونَ إِلَّآ أَن
تَأْتِيَهُمُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ أَوْ يَأْتِىَ أَمْرُ رَبِّكَ ۚ كَذَٰلِكَ فَعَلَ ٱلَّذِينَ مِن
قَبْلِهِمْ ۚ وَمَا ظَلَمَهُمُ ٱللَّهُ وَلَٰكِن كَانُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿٣٣﴾
فَأَصَابَهُمْ سَيِّـَٔاتُ مَا عَمِلُوا۟ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُوا۟ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿٣٤﴾

(27) Sannan kuma ranar alkiyama (Allah) zai kunyata su kuma zai ce: “Ina abokan tarayyar nawa da kuka zamanto kuna jayayya a game da su?” (Sai) waɗanda aka bai wa ilimi su ce: “Lalle a yau wulakanci da mummunar azaba sun tabbata a kan kafirai.”

(28) Waɗanda mala’iku suke karɓar ransu suna masu zaluntar kawunansu; sai suka ba da kai (suna cewa,): “Ba mu kasance muna yin wani mummunan aiki ba.” A’a, ba haka ba ne, lalle Allah Masanin abin da kuka zamanto kuna aikatawa ne

(29) “Sai ku shiga ƙofofin Jahannama kuna masu dawwama a cikinta; lalle makomar masu girman kai ta munana.”

(30) Aka kuma ce da waɗanda suka kiyaye dokokin (Allah): “Me Ubangijinku Ya saukar?” Suka ce: “Alheri.” Waɗanda suka kyautata a wannan duniya suna da kyakkyawar (rayuwa). Lalle kuma gidan lahira shi ya fi alheri. Madalla da gidan masu takawa

(31) Aljannatai ne na jin dadi za su shige su, ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu; suna da duk abin da suka ga dama cikinsu. Kamar haka Allah Yake saka wa masu takawa

(32) Waɗanda mala’iku suke ɗaukar ransu suna tsarkaka, suna cewa: “Aminci ya tabbata a gare ku, ku shiga Aljanna saboda abin da kuka zamanto kuna aikatawa (a duniya)

(33) Shin akwai abin da (mushrikai) suke sauraro in ban da mala’iku su zo musu, ko kuma umarnin Ubangijinka ya zo? Kamar haka waɗanda ke gabaninsu suka aikata. Allah bai zalunce su ba, sai dai kuma kawunansu suka kasance suna zalunta

(34) Sai (sakamakon) mummunan abin da suka aikata ya same su, kuma abin da suke yi wa izgili ya rutsa da su

وَقَالَ ٱلَّذِينَ أَشۡرَكُواْ لَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ مَا عَبَدۡنَا مِن دُونِهِۦ مِن
شَيۡءٖ نَّحۡنُ وَلَآ ءَابَآؤُنَا وَلَا حَرَّمۡنَا مِن دُونِهِۦ مِن شَيۡءٖۚ كَذَٰلِكَ
فَعَلَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ فَهَلۡ عَلَى ٱلرُّسُلِ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ
٣٥ وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ
وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَۖ فَمِنۡهُم مَّنۡ هَدَى ٱللَّهُ وَمِنۡهُم مَّنۡ
حَقَّتۡ عَلَيۡهِ ٱلضَّلَٰلَةُۚ فَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱنظُرُواْ كَيۡفَ
كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ ٣٦ إِن تَحۡرِصۡ عَلَىٰ هُدَىٰهُمۡ
فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي مَن يُضِلُّۖ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ٣٧
وَأَقۡسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهۡدَ أَيۡمَٰنِهِمۡ لَا يَبۡعَثُ ٱللَّهُ مَن يَمُوتُۚ بَلَىٰ
وَعۡدًا عَلَيۡهِ حَقّٗا وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٣٨
لِيُبَيِّنَ لَهُمُ ٱلَّذِي يَخۡتَلِفُونَ فِيهِ وَلِيَعۡلَمَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ
أَنَّهُمۡ كَانُواْ كَٰذِبِينَ ٣٩ إِنَّمَا قَوۡلُنَا لِشَيۡءٍ إِذَآ أَرَدۡنَٰهُ أَن نَّقُولَ
لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ٤٠ وَٱلَّذِينَ هَاجَرُواْ فِي ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مَا ظُلِمُواْ
لَنُبَوِّئَنَّهُمۡ فِي ٱلدُّنۡيَا حَسَنَةٗۖ وَلَأَجۡرُ ٱلۡأٓخِرَةِ أَكۡبَرُۚ لَوۡ كَانُواْ
يَعۡلَمُونَ ٤١ ٱلَّذِينَ صَبَرُواْ وَعَلَىٰ رَبِّهِمۡ يَتَوَكَّلُونَ ٤٢

(35) Waɗanda kuma suka yi shirka suka ce: “Da Allah Ya ga dama da ba mu bauta wa komai ba sai Shi, daga mu har iyayenmu, da kuma ba mu haramta komai ba wanda bai haramta ba.” Kamar haka waɗanda suka gabace su suka aikata. Shin akwai abin da yake a kan manzanni in ban da isar da aike a fili?
(36) Haƙiƙa kuma Mun aiko manzo a kowacce al’umma cewa,: “Ku bauta wa Allah, kuma ku nisanci Ɗagutu[1].” To akwai daga cikinsu waɗanda Allah Ya shiryar, akwai kuma daga cikinsu wanda ɓata ya tabbata a kansa. To ku yi tafiya a bayan ƙasa ku ga yadda ƙarshen masu ƙaryatawa ya kasance
(37) Idan ma kana kwaɗayin shiriyarsu ne, to lalle Allah fa ba Ya shiryar da wanda Ya ɓatar; ba su da kuma wasu mataimaka
(38) Suka kuma rantse da Allah iya rantsuwarsu, (cewa) Allah ba zai tashi wanda ya mutu ba. A’a, ba haka ba ne, alƙawari ne a kansa na gaskiya, sai dai yawancin mutane ba sa sanin (haka)
(39) (Zai tashe su) don Ya bayyana musu abin da suke saɓani game da shi, don kuma kafirai su san cewa, su sun tabbata maƙaryata
(40) Abin da kawai Muke cewa da abu idan Mun nufe shi, sai Mu ce da shi: “Kasance”, sai kawai ya kasance
(41) Waɗanda kuma suka yi hijira saboda Allah bayan an zalunce su lalle za Mu shirya musu kyakkyawar (rayuwa) a duniya; ladan lahira kuma ya fi girma da a ce sun kasance suna sane da (haka)
(42) Waɗanda suka yi haƙuri kuma ga Ubangijinsu kawai suke dogaro

(1) Ɗagutu ana nufin duk wani abu da aka ƙetare iyakokin Allah saboda shi, ta hanyar bautar sa, mutum ne ko aljani ko dutse ko itace.

وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ إِلَّا رِجَالٗا نُّوحِيٓ إِلَيۡهِمۡۖ فَسۡـَٔلُوٓاْ أَهۡلَ
ٱلذِّكۡرِ إِن كُنتُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ ٤٣ بِٱلۡبَيِّنَٰتِ وَٱلزُّبُرِۗ وَأَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ
ٱلذِّكۡرَ لِتُبَيِّنَ لِلنَّاسِ مَا نُزِّلَ إِلَيۡهِمۡ وَلَعَلَّهُمۡ يَتَفَكَّرُونَ ٤٤
أَفَأَمِنَ ٱلَّذِينَ مَكَرُواْ ٱلسَّيِّـَٔاتِ أَن يَخۡسِفَ ٱللَّهُ بِهِمُ ٱلۡأَرۡضَ
أَوۡ يَأۡتِيَهُمُ ٱلۡعَذَابُ مِنۡ حَيۡثُ لَا يَشۡعُرُونَ ٤٥ أَوۡ يَأۡخُذَهُمۡ
فِي تَقَلُّبِهِمۡ فَمَا هُم بِمُعۡجِزِينَ ٤٦ أَوۡ يَأۡخُذَهُمۡ عَلَىٰ تَخَوُّفٖ فَإِنَّ
رَبَّكُمۡ لَرَءُوفٞ رَّحِيمٌ ٤٧ أَوَلَمۡ يَرَوۡاْ إِلَىٰ مَا خَلَقَ ٱللَّهُ مِن شَيۡءٖ
يَتَفَيَّؤُاْ ظِلَٰلُهُۥ عَنِ ٱلۡيَمِينِ وَٱلشَّمَآئِلِ سُجَّدٗا لِّلَّهِ وَهُمۡ دَٰخِرُونَ
٤٨ وَلِلَّهِ يَسۡجُدُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِ مِن دَآبَّةٖ
وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَهُمۡ لَا يَسۡتَكۡبِرُونَ ٤٩ يَخَافُونَ رَبَّهُم مِّن فَوۡقِهِمۡ
وَيَفۡعَلُونَ مَا يُؤۡمَرُونَ ٥٠ ۞ وَقَالَ ٱللَّهُ لَا تَتَّخِذُوٓاْ إِلَٰهَيۡنِ
ٱثۡنَيۡنِۖ إِنَّمَا هُوَ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۖ فَإِيَّٰيَ فَٱرۡهَبُونِ ٥١ وَلَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِ وَلَهُ ٱلدِّينُ وَاصِبًاۚ أَفَغَيۡرَ ٱللَّهِ تَتَّقُونَ ٥٢ وَمَا بِكُم مِّن
نِّعۡمَةٖ فَمِنَ ٱللَّهِۖ ثُمَّ إِذَا مَسَّكُمُ ٱلضُّرُّ فَإِلَيۡهِ تَجۡـَٔرُونَ ٥٣ ثُمَّ إِذَا
كَشَفَ ٱلضُّرَّ عَنكُمۡ إِذَا فَرِيقٞ مِّنكُم بِرَبِّهِمۡ يُشۡرِكُونَ ٥٤

(43) Ba Mu taɓa aiko (wasu manzanni) ba a gabaninka sai mazaje waɗanda Muke yi wa wahayi. Don haka ku tambayi ma'abota ilimi idan kun kasance ba ku sani ba(44) (Mun aiko su) da hujjoji bayyanannu da littattafai. Mun kuma saukar maka da Alƙur'ani don ka yi wa mutane bayanin abin da aka saukar musu ko sa yi tunani(45)Yanzu waɗanda suka shirya mummunan makirci ba sa gudun Allah Ya kife ƙasa da su, ko kuma azaba ta zo musu ta inda ba sa zato?(46) Ko kuwa Ya kama su a cikin kai-kawonsu, ba kuwa za su gagara ba?

(47) Ko kuma Ya kama su a lokacin da suke cike da tsoron (Sa)? To lalle Ubangijinka Mai tausayi ne, Mai jin ƙai
(48) Shin yanzu ba sa ganin abubuwan da Allah Ya halitta kowane iri ne, inuwowinsa suna bazuwa dama da hagu, suna masu sujjada ga Allah suna kuma masu ƙasƙantar da kai(1)?
(49) Abin da yake cikin sammai da abin da yake bayan ƙasa na kowace dabba da mala'iku suna yin sujjada ne ga Allah, su kuma ba sa girman kai
(50) Suna tsoron Ubangijnsu daga samansu kuma suna aikata abin da ake umartar su da shi
(51) Allah kuma Ya ce: "Kada ku riƙi abubuwan bauta guda biyu(2). Abin bauta Ɗaya Yake Tilo; to sai ku ji tsoro na Ni kaɗai."
(52) Kuma abin da ke sammai da ƙasa nasa ne, kuma gare Shi ake biyayya tutur. Shin yanzu wanin Allah ne kuke yi wa taƙawa?
(53) Kuma duk abin da kuke da shi na ni'ima to daga Allah ne; sannan kuma idan cuta ta same ku to wurinsa kuke kai kuka
(54) Sannan kuma lokacin da Ya yaye muku cutar sai a samu wata ƙungiya daga cikinku suna yin shirka da Ubangijinsu

(1) Malamai sun ce, idan rana ta gushe daga tsakiyar sama, to komai yana faɗuwa ya yi sujjada ga Allah.

(2) Watau kamar Majusawa masu cewa, wai akwai ubangijin alheri shi ne haske, akwai kuma na sharri shi ne duhu.

لِيَكْفُرُوا۟ بِمَآ ءَاتَيْنَٰهُمْ ۚ فَتَمَتَّعُوا۟ فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿٥٥﴾ وَيَجْعَلُونَ
لِمَا لَا يَعْلَمُونَ نَصِيبًا مِّمَّا رَزَقْنَٰهُمْ ۗ تَٱللَّهِ لَتُسْـَٔلُنَّ عَمَّا كُنتُمْ
تَفْتَرُونَ ﴿٥٦﴾ وَيَجْعَلُونَ لِلَّهِ ٱلْبَنَٰتِ سُبْحَٰنَهُۥ وَلَهُم مَّا يَشْتَهُونَ
﴿٥٧﴾ وَإِذَا بُشِّرَ أَحَدُهُم بِٱلْأُنثَىٰ ظَلَّ وَجْهُهُۥ مُسْوَدًّا وَهُوَ كَظِيمٌ ﴿٥٨﴾
يَتَوَٰرَىٰ مِنَ ٱلْقَوْمِ مِن سُوٓءِ مَا بُشِّرَ بِهِۦٓ ۚ أَيُمْسِكُهُۥ عَلَىٰ هُونٍ
أَمْ يَدُسُّهُۥ فِى ٱلتُّرَابِ ۗ أَلَا سَآءَ مَا يَحْكُمُونَ ﴿٥٩﴾ لِلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ
بِٱلْءَاخِرَةِ مَثَلُ ٱلسَّوْءِ ۖ وَلِلَّهِ ٱلْمَثَلُ ٱلْأَعْلَىٰ ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ
﴿٦٠﴾ وَلَوْ يُؤَاخِذُ ٱللَّهُ ٱلنَّاسَ بِظُلْمِهِم مَّا تَرَكَ عَلَيْهَا مِن دَآبَّةٍ
وَلَٰكِن يُؤَخِّرُهُمْ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى ۖ فَإِذَا جَآءَ أَجَلُهُمْ لَا يَسْتَـْٔخِرُونَ
سَاعَةً وَلَا يَسْتَقْدِمُونَ ﴿٦١﴾ وَيَجْعَلُونَ لِلَّهِ مَا يَكْرَهُونَ ۖ وَتَصِفُ
أَلْسِنَتُهُمُ ٱلْكَذِبَ أَنَّ لَهُمُ ٱلْحُسْنَىٰ ۚ لَا جَرَمَ أَنَّ لَهُمُ ٱلنَّارَ
وَأَنَّهُم مُّفْرَطُونَ ﴿٦٢﴾ تَٱللَّهِ لَقَدْ أَرْسَلْنَآ إِلَىٰٓ أُمَمٍ مِّن قَبْلِكَ
فَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيْطَٰنُ أَعْمَٰلَهُمْ فَهُوَ وَلِيُّهُمُ ٱلْيَوْمَ وَلَهُمْ
عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٦٣﴾ وَمَآ أَنزَلْنَا عَلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ إِلَّا لِتُبَيِّنَ لَهُمُ
ٱلَّذِى ٱخْتَلَفُوا۟ فِيهِ ۙ وَهُدًى وَرَحْمَةً لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٦٤﴾

(55) Don su butulce wa abin da Muka ba su. To ku ɗan ji dadi a (duniya), sai dai ba da daɗewa ba za ku sani

(56) Suna kuma sanya wani kaso daga abin da Muka arzuta su da shi ga abubuwan da ba su san komai ba. Wallahi tabbas za a tambaye ku game da abin da kuka kasance kuna ƙirƙira

(57) Suna kuma jingina wa Allah ‘ya’ya mata[1], tsarki ya tabbata a gare Shi, su kuma suna da abin da suke sha’awa (na ‘ya’ya maza)

(58) Kuma idan aka yi wa ɗayansu albishir da (‘ya) mace sai fuskarsa ta yi baƙi ƙirin yana cike da tsananin baƙin ciki

mutane saboda munin abin da aka yi masa albishir da shi. Shin zai riƙe shi ne a wulaƙance ko kuwa zai binne shi ne a cikin ƙasa? Ku saurara, abin da suke hukuntawa kam ya munana

(60) Waɗanda ba sa imani da ranar lahira suna da mummunar siffa. Allah kuwa Yana da maɗaukakiyar siffa. Kuma Shi ne Mabuwayi Mai hikima

(61) Da kuwa Allah Yana kama mutane da laifukansu ne to da bai bar wata dabba (mai tafiya) a bayanta ba (wato ƙasa), sai dai kuma Yana saurara musu ne har zuwa wani lokaci ƙayyadajje. To idan ajalinsu ya zo ba za su jinkirta daidai da sa’a guda ba, kuma ba za su gabata ba

(62) Suna kuma sanya wa Allah abin da suke ƙi, kuma harsunansu suna bayanin ƙaryar cewa, suna da mafi kyan sakamako; ba shakka, lalle suna da (sakamakon) wuta, kuma haƙiƙa su waɗanda za a bar su ne (cikinta har abada)

(63) Wallahi haƙiƙa Mun aiko (manzanni) zuwa ga al’ummun da suke gabaninka, sai Shaiɗan ya ƙawata musu ayyukansu, kuma shi ne majiɓincin al’amuransu a yau, kuma suna da azaba mai raɗaɗi

(64) Kuma ba Mu saukar maka da Littafi ba sai don ka yi musu bayanin abin da suka yi saɓani game da shi, kuma shiriya ne da rahama ga mutanen da suke yin imani

(1) Suna cewa mala’iku mata ne kuma ‘ya’yan Allah ne.

وَٱللَّهُ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَحْيَا بِهِ ٱلْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَآ ۚ إِنَّ فِى
ذَٰلِكَ لَءَايَةً لِّقَوْمٍ يَسْمَعُونَ ﴿٦٥﴾ وَإِنَّ لَكُمْ فِى ٱلْأَنْعَٰمِ لَعِبْرَةً ۖ نُّسْقِيكُم
مِّمَّا فِى بُطُونِهِۦ مِنۢ بَيْنِ فَرْثٍ وَدَمٍ لَّبَنًا خَالِصًا سَآئِغًا لِّلشَّٰرِبِينَ
﴿٦٦﴾ وَمِن ثَمَرَٰتِ ٱلنَّخِيلِ وَٱلْأَعْنَٰبِ تَتَّخِذُونَ مِنْهُ سَكَرًا وَرِزْقًا
حَسَنًا ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً لِّقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ﴿٦٧﴾ وَأَوْحَىٰ رَبُّكَ إِلَى ٱلنَّحْلِ
أَنِ ٱتَّخِذِى مِنَ ٱلْجِبَالِ بُيُوتًا وَمِنَ ٱلشَّجَرِ وَمِمَّا يَعْرِشُونَ ﴿٦٨﴾ ثُمَّ
كُلِى مِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ فَٱسْلُكِى سُبُلَ رَبِّكِ ذُلُلًا ۚ يَخْرُجُ مِنۢ بُطُونِهَا
شَرَابٌ مُّخْتَلِفٌ أَلْوَٰنُهُۥ فِيهِ شِفَآءٌ لِّلنَّاسِ ۗ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً لِّقَوْمٍ
يَتَفَكَّرُونَ ﴿٦٩﴾ وَٱللَّهُ خَلَقَكُمْ ثُمَّ يَتَوَفَّىٰكُمْ ۗ وَمِنكُم مَّن يُرَدُّ إِلَىٰٓ
أَرْذَلِ ٱلْعُمُرِ لِكَىْ لَا يَعْلَمَ بَعْدَ عِلْمٍ شَيْـًٔا ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ قَدِيرٌ ﴿٧٠﴾
وَٱللَّهُ فَضَّلَ بَعْضَكُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ فِى ٱلرِّزْقِ ۚ فَمَا ٱلَّذِينَ فُضِّلُوا۟
بِرَآدِّى رِزْقِهِمْ عَلَىٰ مَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُهُمْ فَهُمْ فِيهِ سَوَآءٌ ۚ أَفَبِنِعْمَةِ
ٱللَّهِ يَجْحَدُونَ ﴿٧١﴾ وَٱللَّهُ جَعَلَ لَكُم مِّنْ أَنفُسِكُمْ أَزْوَٰجًا
وَجَعَلَ لَكُم مِّنْ أَزْوَٰجِكُم بَنِينَ وَحَفَدَةً وَرَزَقَكُم مِّنَ
ٱلطَّيِّبَٰتِ ۚ أَفَبِٱلْبَٰطِلِ يُؤْمِنُونَ وَبِنِعْمَتِ ٱللَّهِ هُمْ يَكْفُرُونَ ﴿٧٢﴾

(65) Allah kuma Ya saukar da ruwa daga sama, sai Ya raya ƙasa da shi bayan mutuwarta. Lalle a game da wannan akwai aya ga mutanen da suke ji
(66) Lalle kuma kuna da wata izina a game da dabbobin ni'ima; Muna shayar da ku da abin da yake cikin cikkunansu (mai fitowa) ta tsakankanin uwar hanji da jinni; nono tatacce mai daɗin kwankwaɗa ga masu sha
(67) Daga kuma 'ya'yan dabinai da na inabai kuna yin giya da shi(1) da kuma arziki mai kyau. Lalle a game da wannan akwai aya ga

(68) Ubangijinka kuma Ya kimsa wa ƙudan zuma cewa,: "Ki gina gidaje a duwatsu da kan bishiyoyi da kuma rufin da (mutane) suke yi"
(69) "Sannan kuma ki ci daga kowanne 'ya'yan itace, kuma ki shiga hanyoyin Ubangijinki horarru (gare ki)." Abin sha mai launi daban-daban yana fitowa daga cikin cikinta; a cikinsa (kuma) da akwai waraka ga mutane. Lalle a game da wannan akwai aya ga mutane masu tunani
(70) Kuma Allah ne Ya halicce ku, sannan kuma Shi zai kashe ku. Daga cikinku akwai wanda zai zama tsoho tukuf don kada ya san komai bayan (da can yana da) sani. Lalle Allah Masani ne, Mai iko
(71) Allah kuma Ya fifita sashenku a kan wani sashi a arziki. Waɗanda aka fifita ɗin ba za su ba da arzikin nasu ga bayinsu ba don su zama daidai a cikinsa(2). Shin da ni'imar Allah ne suke jayayya?
(72) Allah kuma Ya sanya muku matan aure daga jinsinku, Ya kuma sanya muku 'ya'yaye da jikoki daga matayen naku, Ya kuma arzuta ku da abubuwa tsarkaka. Yanzu da ƙarya suke yin imani kuma suke kafirce wa ni'imar Allah?

(1) Wannan ayar ta sauka kafin a haramta shan giya. Daga baya Allah ( ) ya haramta duk wani abu mai gusar da hankali.

(2) To me ya sa kafirai suka yarda su sanya wa Allah kishiyoyi daga cikin bayinsa, amma su ba su amince bayinsusu yi tarayya da su a cikin dukiyoyinsu ba?

وَيَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَمْلِكُ لَهُمْ رِزْقًا مِّنَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ شَيْـًٔا وَلَا يَسْتَطِيعُونَ ﴿٧٣﴾ فَلَا تَضْرِبُوا۟ لِلَّهِ ٱلْأَمْثَالَ ۚ
إِنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿٧٤﴾ ۞ ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلًا عَبْدًا
مَّمْلُوكًا لَّا يَقْدِرُ عَلَىٰ شَىْءٍ وَمَن رَّزَقْنَٰهُ مِنَّا رِزْقًا حَسَنًا
فَهُوَ يُنفِقُ مِنْهُ سِرًّا وَجَهْرًا ۖ هَلْ يَسْتَوُۥنَ ۚ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ۚ
بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٧٥﴾ وَضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلًا رَّجُلَيْنِ
أَحَدُهُمَآ أَبْكَمُ لَا يَقْدِرُ عَلَىٰ شَىْءٍ وَهُوَ كَلٌّ عَلَىٰ مَوْلَىٰهُ
أَيْنَمَا يُوَجِّههُّ لَا يَأْتِ بِخَيْرٍ ۖ هَلْ يَسْتَوِى هُوَ ۙ وَمَن يَأْمُرُ
بِٱلْعَدْلِ وَهُوَ عَلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٧٦﴾ وَلِلَّهِ غَيْبُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ وَمَآ أَمْرُ ٱلسَّاعَةِ إِلَّا كَلَمْحِ
ٱلْبَصَرِ أَوْ هُوَ أَقْرَبُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٧٧﴾
وَٱللَّهُ أَخْرَجَكُم مِّنۢ بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمْ لَا تَعْلَمُونَ شَيْـًٔا
وَجَعَلَ لَكُمُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ وَٱلْأَفْـِٔدَةَ ۙ لَعَلَّكُمْ
تَشْكُرُونَ ﴿٧٨﴾ أَلَمْ يَرَوْا۟ إِلَى ٱلطَّيْرِ مُسَخَّرَٰتٍ فِى جَوِّ ٱلسَّمَآءِ
مَا يُمْسِكُهُنَّ إِلَّا ٱللَّهُ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٧٩﴾

(73) Suna kuma bauta wa wasu ba Allah ba, waɗanda ba sa mallakar musu wani arziki a sammai da ƙasa, ba za kuma su iya ba
(74) Kada kuma ku sanya wa Allah abokan tarayya. Lalle Allah Yana sane, ku ne ba ku sani ba
(75) Allah kuma Ya ba da misali da bawan da aka mallaka, ba shi da iko a kan komai, da kuma wanda Muka bai wa arziki nagari daga gare Mu, to shi kuma yana ciyarwa daga shi (arzikin) a ɓoye da kuma sarari; yanzu za su yi daidai? (Ai ba za su ba). To godiya ta tabbata ga Allah. A'a, yawancinsu dai ba su san (haka) ba ne
(76) Allah kuma Ya ba da wani misali da mutum biyu, ɗayansu bebe ne ba ya iya yin komai, kuma ya zama nauyi a kan mai gidansa, duk inda ya fuskantar da shi ba zai zo da wani alheri ba. Yanzu shi zai yi daidai da wanda yake umarni da adalci kuma yana bisa tafarki madaidaici?
(77) Kuma Allah ne Masanin gaibu na sammai da ƙasa. Al'amarin alƙiyama kuma ba komai ba ne face kamar ƙiftawar ido ko kuma ya fi haka kusa. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai
(78) Allah ne kuma Ya fito da ku daga cikkunan iyayenku, ba ku san komai ba, Ya kuma sanya muku ji da gani da kuma zukata don ku gode masa
(79) Yanzu ba sa ganin tsuntsaye da aka lamunce wa (tashi) a sararin sama, ba mai riƙe su sai Allah? Lalle a game da wannan akwai ayoyi ga mutane masu yin imani

وَٱللَّهُ جَعَلَ لَكُمۡ مِّنۢ بُيُوتِكُمۡ سَكَنٗا وَجَعَلَ لَكُم مِّن جُلُودِ
ٱلۡأَنۡعَٰمِ بُيُوتٗا تَسۡتَخِفُّونَهَا يَوۡمَ ظَعۡنِكُمۡ وَيَوۡمَ إِقَامَتِكُمۡ
وَمِنۡ أَصۡوَافِهَا وَأَوۡبَارِهَا وَأَشۡعَارِهَآ أَثَٰثٗا وَمَتَٰعًا إِلَىٰ حِينٖ
٨٠ وَٱللَّهُ جَعَلَ لَكُم مِّمَّا خَلَقَ ظِلَٰلٗا وَجَعَلَ لَكُم مِّنَ
ٱلۡجِبَالِ أَكۡنَٰنٗا وَجَعَلَ لَكُمۡ سَرَٰبِيلَ تَقِيكُمُ
ٱلۡحَرَّ وَسَرَٰبِيلَ تَقِيكُم بَأۡسَكُمۡۚ كَذَٰلِكَ يُتِمُّ نِعۡمَتَهُۥ
عَلَيۡكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تُسۡلِمُونَ ٨١ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَإِنَّمَا عَلَيۡكَ
ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ٨٢ يَعۡرِفُونَ نِعۡمَتَ ٱللَّهِ ثُمَّ يُنكِرُونَهَا
وَأَكۡثَرُهُمُ ٱلۡكَٰفِرُونَ ٨٣ وَيَوۡمَ نَبۡعَثُ مِن كُلِّ أُمَّةٖ
شَهِيدٗا ثُمَّ لَا يُؤۡذَنُ لِلَّذِينَ كَفَرُواْ وَلَا هُمۡ يُسۡتَعۡتَبُونَ
٨٤ وَإِذَا رَءَا ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ ٱلۡعَذَابَ فَلَا يُخَفَّفُ عَنۡهُمۡ وَلَا هُمۡ
يُنظَرُونَ ٨٥ وَإِذَا رَءَا ٱلَّذِينَ أَشۡرَكُواْ شُرَكَآءَهُمۡ قَالُواْ
رَبَّنَا هَٰٓؤُلَآءِ شُرَكَآؤُنَا ٱلَّذِينَ كُنَّا نَدۡعُواْ مِن دُونِكَۖ
فَأَلۡقَوۡاْ إِلَيۡهِمُ ٱلۡقَوۡلَ إِنَّكُمۡ لَكَٰذِبُونَ ٨٦ وَأَلۡقَوۡاْ إِلَى
ٱللَّهِ يَوۡمَئِذٍ ٱلسَّلَمَۖ وَضَلَّ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ ٨٧

(80) Allah ne kuma Ya sanya muku gidajenku wuraren hutawarku, Ya kuma sanya muku gidaje daga fatun dabbobin ni'ima, kuna ɗaukar su ba nauyi a ranar tafiyarku da ranar saukarku. Daga kuma gashin (tumaki) da gashin rakuma da gashin (awaki, Ya sanya muku) kayan shimfiɗa da kuma (kayan) jin dadi zuwa wani ɗan lokaci

(81) Kuma Allah ne Ya sanya muku inuwoyi daga abin da Ya halitta, Ya kuma sanya muku ɗakuna daga duwatsu, Ya kuma sanya muku riguna da suke kare ku daga zafi, da kuma riguna (na sulke) da suke kare ku (daga makamai) a fagen daga. Kamar haka ne Yake cika muku ni'imarsa don ku miƙa wuya

(82) To idan suka ba da baya, to kai isar da aike a fili ne kawai a kanka

(83) Suna sane da ni'imar Allah sannan sai su musanta ta, yawancinsu kuwa kafirai ne

(84) Kuma (ka tuna) ranar da za Mu tayar da mai shaida daga kowacce al'umma, sannan ba za a yi wa waɗanda suka kafirta izini ba, ba kuwa za a karɓi uzurin nasu ba

(85) Idan kuma waɗanda suka kafirta suka ga azaba, to ba za a sauƙaƙa musu ba, ba kuma za a saurara musu ba

(86) Idan kuma waɗanda suka yi tarayya (da Allah) suka ga ababen tarayyarsu (sai) su ce: "Ya Ubangijinmu, waɗannan su ne ababen tarayyarmu waɗanda muka zamanto muna bauta wa ba Kai ba." Sai su jefa musu magana (cewa,): "Ku dai lalle maƙaryata ne!"

(87) Kuma a wannan ranar suka miƙa wuya ga Allah; kuma duk abin da suka zamanto suna ƙirƙira ya ɓace musu

16 Sura Nahl Izifi 28 Juzu'i 14

ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَصَدُّوا۟ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ زِدْنَٰهُمْ عَذَابًا
فَوْقَ ٱلْعَذَابِ بِمَا كَانُوا۟ يُفْسِدُونَ ﴿٨٨﴾ وَيَوْمَ نَبْعَثُ فِى
كُلِّ أُمَّةٍ شَهِيدًا عَلَيْهِم مِّنْ أَنفُسِهِمْ ۖ وَجِئْنَا بِكَ
شَهِيدًا عَلَىٰ هَٰٓؤُلَآءِ ۚ وَنَزَّلْنَا عَلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ تِبْيَٰنًا لِّكُلِّ
شَىْءٍ وَهُدًى وَرَحْمَةً وَبُشْرَىٰ لِلْمُسْلِمِينَ ﴿٨٩﴾ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ
يَأْمُرُ بِٱلْعَدْلِ وَٱلْإِحْسَٰنِ وَإِيتَآئِ ذِى ٱلْقُرْبَىٰ وَيَنْهَىٰ عَنِ
ٱلْفَحْشَآءِ وَٱلْمُنكَرِ وَٱلْبَغْىِ ۚ يَعِظُكُمْ لَعَلَّكُمْ تَذَكَّرُونَ
﴿٩٠﴾ وَأَوْفُوا۟ بِعَهْدِ ٱللَّهِ إِذَا عَٰهَدتُّمْ وَلَا تَنقُضُوا۟ ٱلْأَيْمَٰنَ
بَعْدَ تَوْكِيدِهَا وَقَدْ جَعَلْتُمُ ٱللَّهَ عَلَيْكُمْ كَفِيلًا ۚ إِنَّ
ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا تَفْعَلُونَ ﴿٩١﴾ وَلَا تَكُونُوا۟ كَٱلَّتِى نَقَضَتْ
غَزْلَهَا مِنۢ بَعْدِ قُوَّةٍ أَنكَٰثًا تَتَّخِذُونَ أَيْمَٰنَكُمْ دَخَلًۢا
بَيْنَكُمْ أَن تَكُونَ أُمَّةٌ هِىَ أَرْبَىٰ مِنْ أُمَّةٍ ۚ إِنَّمَا يَبْلُوكُمُ ٱللَّهُ
بِهِۦ ۚ وَلَيُبَيِّنَنَّ لَكُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ مَا كُنتُمْ فِيهِ تَخْتَلِفُونَ
﴿٩٢﴾ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَكُمْ أُمَّةً وَٰحِدَةً وَلَٰكِن يُضِلُّ مَن
يَشَآءُ وَيَهْدِى مَن يَشَآءُ ۚ وَلَتُسْـَٔلُنَّ عَمَّا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٩٣﴾

(88) Waɗanda suka kafirta suka kuma toshe hanyar Allah, to Mun ƙara musu azaba a kan azabar (da suka cancance ta) saboda ɓarnar da suka zamanto suna yi
(89) Kuma (ka tuna) ranar da za Mu tayar wa kowace al'umma da mai ba da shaida a kansu daga jinsinsu, Mu kuma zo da kai (Annabi Muhammadu) shaida a kan waɗannan (wato al'ummarka). Kuma Mun saukar maka da Littafi ne (wato Alƙur'ani) don bayani ga kowanne abu, kuma shiriya da rahama da bushara ga Musulmi da yin adalci da kyautatawa da kuma bai wa makusanta (taimako), Yana kuma hana alfasha da mummunan aiki da zalunci. Yana gargaɗin ku don ku wa'azantu
(91) Ku kuma cika alƙawarin Allah idan kuka ɗauki alƙawari, kada kuma ku warware rantsuwa bayan kun ƙarfafa ta, alhali kuwa kun sanya Allah shaida a kanku. Lalle Allah Yana sane da abin da kuke aikatawa
(92) Kada kuma ku zamanto kamar (mace) wadda ta warware kaɗinta wara-wara bayan ƙarfinsa, kuna ɗaukar rantse-rantsenku yaudara a tsakaninku, don ganin kasancewar wata al'umma ta fi wata yawa da ƙarfi. Allah dai Yana jarabtar ku da shi (cika alƙawari) ne. Don kuma a ranar alƙiyama Ya bayyana muku abin da kuka kasance kuna saɓani a game da shi
(93) Da kuwa Allah Ya ga dama da Ya sanya ku al'umma ɗaya (masu addini ɗaya), sai dai kuma Yana ɓatar da wanda Ya ga dama Yana kuma shiryar da wanda Ya ga dama. Kuma tabbas za a tambaye ku game da abin da kuka kasance kuna aikatawa

وَلَا تَتَّخِذُوٓا۟ أَيْمَـٰنَكُمْ دَخَلًۢا بَيْنَكُمْ فَتَزِلَّ قَدَمٌۢ بَعْدَ
ثُبُوتِهَا وَتَذُوقُوا۟ ٱلسُّوٓءَ بِمَا صَدَدتُّمْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَكُمْ
عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿٩٤﴾ وَلَا تَشْتَرُوا۟ بِعَهْدِ ٱللَّهِ ثَمَنًا قَلِيلًا ۚ إِنَّمَا
عِندَ ٱللَّهِ هُوَ خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٩٥﴾ مَا عِندَكُمْ
يَنفَدُ ۖ وَمَا عِندَ ٱللَّهِ بَاقٍ ۗ وَلَنَجْزِيَنَّ ٱلَّذِينَ صَبَرُوٓا۟ أَجْرَهُم
بِأَحْسَنِ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٩٦﴾ مَنْ عَمِلَ صَـٰلِحًا
مِّن ذَكَرٍ أَوْ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَلَنُحْيِيَنَّهُۥ حَيَوٰةً طَيِّبَةً ۖ
وَلَنَجْزِيَنَّهُمْ أَجْرَهُم بِأَحْسَنِ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٩٧﴾
فَإِذَا قَرَأْتَ ٱلْقُرْءَانَ فَٱسْتَعِذْ بِٱللَّهِ مِنَ ٱلشَّيْطَـٰنِ ٱلرَّجِيمِ
﴿٩٨﴾ إِنَّهُۥ لَيْسَ لَهُۥ سُلْطَـٰنٌ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَلَىٰ رَبِّهِمْ
يَتَوَكَّلُونَ ﴿٩٩﴾ إِنَّمَا سُلْطَـٰنُهُۥ عَلَى ٱلَّذِينَ يَتَوَلَّوْنَهُۥ وَٱلَّذِينَ
هُم بِهِۦ مُشْرِكُونَ ﴿١٠٠﴾ وَإِذَا بَدَّلْنَآ ءَايَةً مَّكَانَ ءَايَةٍ
وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا يُنَزِّلُ قَالُوٓا۟ إِنَّمَآ أَنتَ مُفْتَرٍۭ ۚ بَلْ أَكْثَرُهُمْ
لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٠١﴾ قُلْ نَزَّلَهُۥ رُوحُ ٱلْقُدُسِ مِن رَّبِّكَ بِٱلْحَقِّ
لِيُثَبِّتَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَهُدًى وَبُشْرَىٰ لِلْمُسْلِمِينَ ﴿١٠٢﴾

(94) Kuma kada ku ɗauki rantse-rantsenku yaudara a tsakaninku, sai ƙafafuwanku su zame bayan tabbatarsu, kuma ku ɗanɗani azaba saboda toshe hanyar Allah da kuka yi; kuma (a lahira) kuna da azaba mai girma
(95) Kada kuma ku sayar da alƙawarin Allah da ɗan kuɗi ƙanƙani. Lalle abin da yake wurin Allah shi ya fi muku alheri in kun kasance kun san (haka)
(96) Abin da yake wurinku yana ƙarewa; abin da kuwa yake wurin Allah wanzajje ne. Lalle kuwa tabbas za Mu saka wa waɗanda suka yi haƙuri ladansu da mafi kyan abin da suka kasance suna aikatawa
(97) Wanda ya yi kyakkyawan aiki namiji ko mace alhali shi yana mumini, to lalle za Mu raya shi rayuwa mai daɗi, kuma za Mu saka musu ladansu da mafi kyan abin da suka kasance suna aikatawa
(98) To idan za ka karanta Alƙur'ani sai ka nemi tsarin Allah daga Shaiɗan korarre (daga rahamar Allah)
(99) Lalle shi (Shaiɗan) ba shi da iko a kan waɗanda suka yi imani kuma suke dogara da Ubangijinsu
(100) Ikonsa kawai yana kan waɗanda suke jiɓintar sa da kuma waɗanda suke yin tarayya da shi
(101) Idan kuma Muka musanya wata aya a madadin wata ayar, alhali kuwa Allah ne Mafi sanin abin da Yake saukarwa, sai su ce: "Kai dai mai ƙirƙirar ƙarya ne kawai!" A'a, ba haka ba ne, yawancinsu ba su san (komai) ba ne
(102) Ka ce: "Ruhul Kudusi (watau Mala'ika Jibrilu) ne ya saukar da shi daga Ubangijinka da gaskiya don ya tabbatar da waɗanda suka yi imani (a kan dugadugansu), kuma shiriya ne da albishir ga Musulmai."

وَلَقَدْ نَعْلَمُ أَنَّهُمْ يَقُولُونَ إِنَّمَا يُعَلِّمُهُۥ بَشَرٌ ۗ لِّسَانُ
ٱلَّذِى يُلْحِدُونَ إِلَيْهِ أَعْجَمِىٌّ وَهَٰذَا لِسَانٌ عَرَبِىٌّ مُّبِينٌ
١٠٣ إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ لَا يَهْدِيهِمُ ٱللَّهُ
وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ١٠٤ إِنَّمَا يَفْتَرِى ٱلْكَذِبَ ٱلَّذِينَ
لَا يُؤْمِنُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْكَٰذِبُونَ ١٠٥
مَن كَفَرَ بِٱللَّهِ مِنۢ بَعْدِ إِيمَٰنِهِۦٓ إِلَّا مَنْ أُكْرِهَ وَقَلْبُهُۥ
مُطْمَئِنٌّۢ بِٱلْإِيمَٰنِ وَلَٰكِن مَّن شَرَحَ بِٱلْكُفْرِ
صَدْرًا فَعَلَيْهِمْ غَضَبٌ مِّنَ ٱللَّهِ وَلَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ
١٠٦ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمُ ٱسْتَحَبُّوا۟ ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا عَلَى
ٱلْءَاخِرَةِ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْكَٰفِرِينَ
١٠٧ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ طَبَعَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ وَسَمْعِهِمْ
وَأَبْصَٰرِهِمْ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْغَٰفِلُونَ ١٠٨ لَا جَرَمَ
أَنَّهُمْ فِى ٱلْءَاخِرَةِ هُمُ ٱلْخَٰسِرُونَ ١٠٩ ثُمَّ إِنَّ رَبَّكَ
لِلَّذِينَ هَاجَرُوا۟ مِنۢ بَعْدِ مَا فُتِنُوا۟ ثُمَّ جَٰهَدُوا۟
وَصَبَرُوٓا۟ إِنَّ رَبَّكَ مِنۢ بَعْدِهَا لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ ١١٠

(103) Kuma haƙiƙa Mun san lalle suna cewa,: “Wani mutun ne kawai yake koya masa shi[1].” Harshen wanda suke karkata zuwa gare shi ajami ne, wannan kuwa harshe ne na Larabci bayyananne

(104) Lalle waɗanda ba sa yin imani da ayoyin Allah, to Allah ba zai shirye su ba, kuma suna da azaba mai raɗaɗi

(105) Waɗanda ba sa yin imani da ayoyin Allah su ne kawai suke ƙirƙirar ƙarya; kuma waɗannan su ne maƙaryata

(106) Wanda ya kafirce wa Allah bayan imaninsa, sai dai wanda aka tilasta wa alhali kuwa zuciyarsa ta cika da imani, amma kuma wanda ya buɗe wa kafirci ƙirjinsa, to (waɗannan) fushin Allah ya tabbata a kansu kuma suna da azaba mai girma


(107) Wannan kuwa (ya faru) saboda su sun fi son rayuwar duniya a kan ta lahira, kuma lalle Allah ba Ya shiryar da mutane kafirai

(108) Waɗannan su ne waɗanda Allah Ya doɗe zukatansu da jinsu da ganinsu, kuma waɗannan su ne gafalallu

(109) Ba shakka lalle su a lahira su ne taɓaɓɓu

(110) Sannan lalle Ubangjinka (Mai gafara ne da jin ƙai) ga waɗanda suka yi hijira bayan an fitine su, sannan suka yi jihadi suka kuma yi haƙuri, lalle Ubangijinka, bayansu (waɗannan ayyuka) Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(1) Kuraishawa suka riƙa tuhumar Manzon Allah ( ) yayin da suka gan shi yana magana da wani bawa matashi ba’ajame, suna cewa wai shi ne yake koya masa karatun Alƙur’ani.


* يَوْمَ تَأْتِي كُلُّ نَفْسٍ تُجَٰدِلُ عَن نَّفْسِهَا وَتُوَفَّىٰ كُلُّ
نَفْسٍ مَّا عَمِلَتْ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿١١١﴾ وَضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلًا
قَرْيَةً كَانَتْ ءَامِنَةً مُّطْمَئِنَّةً يَأْتِيهَا رِزْقُهَا رَغَدًا مِّن
كُلِّ مَكَانٍ فَكَفَرَتْ بِأَنْعُمِ ٱللَّهِ فَأَذَٰقَهَا ٱللَّهُ لِبَاسَ
ٱلْجُوعِ وَٱلْخَوْفِ بِمَا كَانُوا۟ يَصْنَعُونَ ﴿١١٢﴾ وَلَقَدْ جَآءَهُمْ
رَسُولٌ مِّنْهُمْ فَكَذَّبُوهُ فَأَخَذَهُمُ ٱلْعَذَابُ وَهُمْ ظَٰلِمُونَ
﴿١١٣﴾ فَكُلُوا۟ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ حَلَٰلًا طَيِّبًا وَٱشْكُرُوا۟
نِعْمَتَ ٱللَّهِ إِن كُنتُمْ إِيَّاهُ تَعْبُدُونَ ﴿١١٤﴾ إِنَّمَا حَرَّمَ
عَلَيْكُمُ ٱلْمَيْتَةَ وَٱلدَّمَ وَلَحْمَ ٱلْخِنزِيرِ وَمَآ أُهِلَّ لِغَيْرِ
ٱللَّهِ بِهِۦ ۖ فَمَنِ ٱضْطُرَّ غَيْرَ بَاغٍ وَلَا عَادٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ
رَّحِيمٌ ﴿١١٥﴾ وَلَا تَقُولُوا۟ لِمَا تَصِفُ أَلْسِنَتُكُمُ ٱلْكَذِبَ
هَٰذَا حَلَٰلٌ وَهَٰذَا حَرَامٌ لِّتَفْتَرُوا۟ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ ۚ إِنَّ
ٱلَّذِينَ يَفْتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ لَا يُفْلِحُونَ ﴿١١٦﴾ مَتَٰعٌ قَلِيلٌ
وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿١١٧﴾ وَعَلَى ٱلَّذِينَ هَادُوا۟ حَرَّمْنَا مَا قَصَصْنَا عَلَيْكَ
مِن قَبْلُ ۖ وَمَا ظَلَمْنَٰهُمْ وَلَٰكِن كَانُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿١١٨﴾

(111) Ranar da kowanne rai zai zo yana kare kansa, kuma a cika wa kowanne rai (sakamakon) abin da ya aikata, kuma su ba za a zalunce su ba

(112) Allah kuma Ya ba da misali da wata alƙarya[1] wadda ta kasance cikin aminci da kwanciyar hankali, arzikinta yana zo mata a yalwace ta kowanne wuri, sai ta kafirce wa ni'imomin Allah, to sai Allah Ya ɗanɗana mata masifar yunwa da tsoro saboda abin da suka kasance suna aikatawa

(113) Haƙiƙa kuma Manzo ya zo musu daga cikinsu, sai suka ƙaryata shi, to sai azaba ta afka musu alhali suna azzalumai

(114) To ku ci halal mai daɗi daga abin da Allah Ya arzuta ku da shi, kuma ku gode ni'imomin Allah in kun kasance Shi kaɗai kuke bauta wa

(115) Abin da kawai Ya haramta muku (shi ne) mushe da jini (mai kwarara) da naman alade da kuma abin da aka yanka da (sunan) wanin Allah; amma wanda ya matsu (ya ci) ba yana mai zalunci ko ƙetare iyaka ba, to lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(116) Kuma saboda abin da harsunanku suke bayyanawa na ƙarya kada ku riƙa cewa, wannan halal ne, wannan kuma haram ne, don ku yi wa Allah ƙarya. Lalle waɗanda suke ƙirƙira wa Allah ƙarya ba sa rabauta

(117) (Wannan) jin daɗi ne ƙanƙani (a duniya), kuma suna da azaba mai raɗaɗi

(118) Kuma Mun haramta wa Yahudawa abin da Muka labarta maka tun tuni[2]; ba Mu kuwa zalunce su ba, sai dai kuma kansu suka zalunta

(1) Watau garin Makka.

(2) Shi ne abin da ya zo a ciki Suratul An'am, aya ta 146.

ثُمَّ إِنَّ رَبَّكَ لِلَّذِينَ عَمِلُوا السُّوءَ بِجَهَٰلَةٍ ثُمَّ تَابُوا مِنۢ بَعْدِ
ذَٰلِكَ وَأَصْلَحُوٓا إِنَّ رَبَّكَ مِنۢ بَعْدِهَا لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١١٩﴾ إِنَّ
إِبْرَٰهِيمَ كَانَ أُمَّةً قَانِتًا لِّلَّهِ حَنِيفًا وَلَمْ يَكُ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ
﴿١٢٠﴾ شَاكِرًا لِّأَنْعُمِهِ ۚ ٱجْتَبَىٰهُ وَهَدَىٰهُ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ
﴿١٢١﴾ وَءَاتَيْنَٰهُ فِى ٱلدُّنْيَا حَسَنَةً ۖ وَإِنَّهُۥ فِى ٱلْءَاخِرَةِ لَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ
﴿١٢٢﴾ ثُمَّ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ أَنِ ٱتَّبِعْ مِلَّةَ إِبْرَٰهِيمَ حَنِيفًا ۖ وَمَا كَانَ
مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿١٢٣﴾ إِنَّمَا جُعِلَ ٱلسَّبْتُ عَلَى ٱلَّذِينَ ٱخْتَلَفُوا
فِيهِ ۚ وَإِنَّ رَبَّكَ لَيَحْكُمُ بَيْنَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فِيمَا
كَانُوا فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿١٢٤﴾ ٱدْعُ إِلَىٰ سَبِيلِ رَبِّكَ بِٱلْحِكْمَةِ
وَٱلْمَوْعِظَةِ ٱلْحَسَنَةِ ۖ وَجَٰدِلْهُم بِٱلَّتِى هِىَ أَحْسَنُ ۚ إِنَّ
رَبَّكَ هُوَ أَعْلَمُ بِمَن ضَلَّ عَن سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعْلَمُ بِٱلْمُهْتَدِينَ
﴿١٢٥﴾ وَإِنْ عَاقَبْتُمْ فَعَاقِبُوا بِمِثْلِ مَا عُوقِبْتُم بِهِۦ ۖ وَلَئِن
صَبَرْتُمْ لَهُوَ خَيْرٌ لِّلصَّٰبِرِينَ ﴿١٢٦﴾ وَٱصْبِرْ وَمَا صَبْرُكَ
إِلَّا بِٱللَّهِ ۚ وَلَا تَحْزَنْ عَلَيْهِمْ وَلَا تَكُ فِى ضَيْقٍ مِّمَّا يَمْكُرُونَ
﴿١٢٧﴾ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوا وَّٱلَّذِينَ هُم مُّحْسِنُونَ ﴿١٢٨﴾

(119) Sannan lalle Ubangijinka (Mai gafara ne) ga waɗanda suka aikata mummuna a cikin jahilci sannan suka tuba bayan haka suka kuma gyara, lalle Ubagijinka Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(120) Lalle Ibrahimu ya zama abin koyi ne mai biyayya ga Allah mai kauce wa ɓarna, bai kuma zamanto daga masu shirka ba

(121) Mai godiya ne ga ni'imarsa (wato Allah), Ya zaɓe shi, Ya kuma shirye shi zuwa ga tafarki madaidaici

(122) Mun kuma ba shi kyakkyawa a duniya; lalle kuma shi a lahira tabbas yana daga cikin salihai

(123) Sannan Muka yi maka wahayi cewa, ka bi addinin Ibrahimu mai kauce wa ɓarna; bai kuwa zamanto daga masu shirka ba

(124) An farlanta (girmama ranar) Asabar kawai a kan waɗanda suka yi saɓani game da ita. kuma lalle Ubangijinka tabbas zai yi hukunci tsakaninsu ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna saɓani a game da shi

(125) Ka yi kira zuwa ga tafarkin Ubangiijnka cikin hikima da kyakkyawan wa'azi, ka kuma yi jayayya da su ta hanyar da ta fi kyau. Lalle Ubangijinka Shi ne Mafi sanin wanda ya ɓace daga hanyarsa, kuma Shi ne Mafi sanin shiryayyu

(126) Idan za ku yi uƙuba to ku yi uƙuba da kwatankwacin abin da aka yi muku uƙuba da shi. Kuma lalle idan kuka yi haƙuri to tabbas shi ne ya fi alheri ga masu haƙuri

(127) Kuma ka yi haƙuri, ba kuwa za ka iya haƙurin ba sai da taimakon Allah. Kada ranka ya ɓaci a kansu, kada kuma ka zama cikin ƙunci game da makircin da suke ƙullawa

(128) Lalle Allah Yana tare da waɗanda suka yi taƙawa da kuma waɗanda suke masu kyautatawa ne

Sura Isra'i

سُورَةُ الإِسْرَاءِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

سُبْحَانَ الَّذِي أَسْرَىٰ بِعَبْدِهِ لَيْلًا مِّنَ الْمَسْجِدِ الْحَرَامِ إِلَى
الْمَسْجِدِ الْأَقْصَا الَّذِي بَارَكْنَا حَوْلَهُ لِنُرِيَهُ مِنْ آيَاتِنَا ۚ إِنَّهُ
هُوَ السَّمِيعُ الْبَصِيرُ ﴿١﴾ وَآتَيْنَا مُوسَى الْكِتَابَ وَجَعَلْنَاهُ
هُدًى لِّبَنِي إِسْرَائِيلَ أَلَّا تَتَّخِذُوا مِن دُونِي وَكِيلًا ﴿٢﴾
ذُرِّيَّةَ مَنْ حَمَلْنَا مَعَ نُوحٍ ۚ إِنَّهُ كَانَ عَبْدًا شَكُورًا ﴿٣﴾
وَقَضَيْنَا إِلَىٰ بَنِي إِسْرَائِيلَ فِي الْكِتَابِ لَتُفْسِدُنَّ فِي الْأَرْضِ
مَرَّتَيْنِ وَلَتَعْلُنَّ عُلُوًّا كَبِيرًا ﴿٤﴾ فَإِذَا جَاءَ وَعْدُ أُولَاهُمَا
بَعَثْنَا عَلَيْكُمْ عِبَادًا لَّنَا أُولِي بَأْسٍ شَدِيدٍ فَجَاسُوا خِلَالَ
الدِّيَارِ ۚ وَكَانَ وَعْدًا مَّفْعُولًا ﴿٥﴾ ثُمَّ رَدَدْنَا لَكُمُ الْكَرَّةَ
عَلَيْهِمْ وَأَمْدَدْنَاكُم بِأَمْوَالٍ وَبَنِينَ وَجَعَلْنَاكُمْ أَكْثَرَ نَفِيرًا
﴿٦﴾ إِنْ أَحْسَنتُمْ أَحْسَنتُمْ لِأَنفُسِكُمْ ۖ وَإِنْ أَسَأْتُمْ فَلَهَا ۚ فَإِذَا
جَاءَ وَعْدُ الْآخِرَةِ لِيَسُوءُوا وُجُوهَكُمْ وَلِيَدْخُلُوا الْمَسْجِدَ
كَمَا دَخَلُوهُ أَوَّلَ مَرَّةٍ وَلِيُتَبِّرُوا مَا عَلَوْا تَتْبِيرًا ﴿٧﴾

(1) Tsarki ya tabbata ga wanda Ya yi Isra'i da bawansa cikin dare daga Masallaci mai alfarma[1] zuwa Masallaci mafi nisa (na Kudus) wanda Muka albarkaci kewayensa, don Mu nuna masa wasu daga ayoyinmu. Lalle Shi Mai ji ne, Mai gani

(2) Kuma Mun bai wa Musa Littafi Muka kuma sanya shi ya zama shiriya ga Banu Isra'ila cewa: "Kada ku riki wani wakili ba ni ba."

(3) (Ya ku) zurriyar wadanda Muka dauko tare da Nuhu (a cikin jirgi). Lalle shi ya zamanto bawa ne mai yawan godiya

(4) Muka kuma kaddara ga Banu Isra'ila cikin Littafin (Attaura) cewa: "Lalle tabbas za ku yi barna a bayan kasa sau biyu, kuma lalle tabbas za ku yi girman kai mai tsanani

(5) "To idan alkawarin ta farkonsu (barna) ya zo sai Mu aiko muku da bayinmu masu tsananin karfi sai su kutsa tsakiyar gidajen (naku). Kuma (wannan) ya zamanto alkawari ne mai faruwa

(6) "Sannan kuma Muka ba ku damar galaba a kansu, Muka kuma kare ku da dukiyoyi da 'ya'ya, Muka kuma sanya ku kuka zama mafi yawan jama'a

(7) "Idan kun kyautata to kanku kuka kyautata wa, idan kuma kuka munana to kanku kuka yi wa. To idan alkawarin (barnar) ta karshe ya zo (sai makiyanku su zo) don su wulakanta ku su kuma shiga masallaci (na Baitul Makadis) kamar yadda suka shige shi tun farko, kuma za su yi raga-raga da (duk) abin da suka biyo ta kansa

(1) Watau masallacin Ka'aba da yake Makka.

عَسَىٰ رَبُّكُمْ أَن يَرْحَمَكُمْ ۚ وَإِنْ عُدتُّمْ عُدْنَا ۘ وَجَعَلْنَا جَهَنَّمَ لِلْكَٰفِرِينَ
حَصِيرًا ﴿٨﴾ إِنَّ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانَ يَهْدِى لِلَّتِى هِىَ أَقْوَمُ وَيُبَشِّرُ
ٱلْمُؤْمِنِينَ ٱلَّذِينَ يَعْمَلُونَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أَنَّ لَهُمْ أَجْرًا كَبِيرًا ﴿٩﴾
وَأَنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِٱلْءَاخِرَةِ أَعْتَدْنَا لَهُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿١٠﴾
وَيَدْعُ ٱلْإِنسَٰنُ بِٱلشَّرِّ دُعَآءَهُۥ بِٱلْخَيْرِ ۖ وَكَانَ ٱلْإِنسَٰنُ عَجُولًا ﴿١١﴾
وَجَعَلْنَا ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ ءَايَتَيْنِ ۖ فَمَحَوْنَآ ءَايَةَ ٱلَّيْلِ وَجَعَلْنَآ ءَايَةَ
ٱلنَّهَارِ مُبْصِرَةً لِّتَبْتَغُوا۟ فَضْلًا مِّن رَّبِّكُمْ وَلِتَعْلَمُوا۟ عَدَدَ
ٱلسِّنِينَ وَٱلْحِسَابَ ۚ وَكُلَّ شَىْءٍ فَصَّلْنَٰهُ تَفْصِيلًا ﴿١٢﴾ وَكُلَّ
إِنسَٰنٍ أَلْزَمْنَٰهُ طَٰٓئِرَهُۥ فِى عُنُقِهِۦ ۖ وَنُخْرِجُ لَهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ كِتَٰبًا
يَلْقَىٰهُ مَنشُورًا ﴿١٣﴾ ٱقْرَأْ كِتَٰبَكَ كَفَىٰ بِنَفْسِكَ ٱلْيَوْمَ عَلَيْكَ حَسِيبًا
﴿١٤﴾ مَّنِ ٱهْتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهْتَدِى لِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَن ضَلَّ فَإِنَّمَا يَضِلُّ
عَلَيْهَا ۚ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٌ وِزْرَ أُخْرَىٰ ۗ وَمَا كُنَّا مُعَذِّبِينَ حَتَّىٰ نَبْعَثَ
رَسُولًا ﴿١٥﴾ وَإِذَآ أَرَدْنَآ أَن نُّهْلِكَ قَرْيَةً أَمَرْنَا مُتْرَفِيهَا فَفَسَقُوا۟ فِيهَا
فَحَقَّ عَلَيْهَا ٱلْقَوْلُ فَدَمَّرْنَٰهَا تَدْمِيرًا ﴿١٦﴾ وَكَمْ أَهْلَكْنَا مِنَ ٱلْقُرُونِ
مِنۢ بَعْدِ نُوحٍ ۗ وَكَفَىٰ بِرَبِّكَ بِذُنُوبِ عِبَادِهِۦ خَبِيرًۢا بَصِيرًا ﴿١٧﴾

(8) "Mai yiwuwa ne Ubangijinku ya ji ƙan ku. (Amma) kuma idan kuka dawo (kan ɓarnar sai) Mu dawo (da azabtar da ku). Mun kuma sanya Jahannama ta zama shimfiɗa ga kafirai."
(9) Lalle wannan Alƙur'anin yana shiryarwa ne ga (hanya) mafi miƙewa, yana kuma yi wa muminai waɗanda suke yin kyawawan ayyuka albishir cewa, lalle suna da lada mai girma
(10) Waɗanda kuwa ba su yi imani da ranar lahira ba lalle Mun tanadar musu azaba mai raɗaɗi

(11) Kuma mutum yakan roƙi sharri[1] kamar yadda yake roƙon alheri; mutum kuwa ya zamanto mai gaggawa ne
(12) Muka kuma sanya dare da rana su zama ayoyi guda biyu; sai Muka shafe ayar dare (ta zama duhu) Muka kuma sanya ayar rana ta zama mai haskakawa, don ku nemi falala daga Ubangijinku, don kuma ku san yawan shekaru da lissafi. Kowane abu kuwa Mun rarrabe shi filla-filla
(13) Kuma kowane mutum Mun ɗaura masa littafin aikinsa a wuyansa, za kuma Mu fito masa da wani littafi a ranar alƙiyama da zai same shi a buɗe
(14) (A ce da shi): "Karanta littafinka; a yau ka isa ka yi wa kanka hukunci da kanka."
(15) Wanda ya shiriya to lalle yana shiriya ne don kansa; wanda kuwa ya ɓata to lalle yana ɓata ne don kansa. Ba kuwa wanda zai ɗauki nauyin laifin wani. Kuma ba Mu zamanto Masu azabtarwa ba har sai Mun aiko da manzo
(16) Idan Muka nufi hallakar da wata alƙarya sai Mu sanya 'yan ta-moren cikinta su aikata fasiƙanci a cikinta, sai kalmar azaba ta tabbata a kanta (watau alƙaryar) sai Mu rugurguza ta ragaraga
(17) Al'umma nawa ne Muka hallaka bayan Nuhu? Kuma ai ya isa Ubangijinka Ya zamana Mai cikakken sani ne da gani ga zunuban bayinsa

(1) Watau idan ya yi fushi yakan yi wa kansa ko 'ya'yansa ko dukiyarsa mummunar addu'a.

مَّن كَانَ يُرِيدُ ٱلْعَاجِلَةَ عَجَّلْنَا لَهُۥ فِيهَا مَا نَشَآءُ لِمَن نُّرِيدُ ثُمَّ
جَعَلْنَا لَهُۥ جَهَنَّمَ يَصْلَىٰهَا مَذْمُومًا مَّدْحُورًا ﴿١٨﴾ وَمَنْ أَرَادَ
ٱلْءَاخِرَةَ وَسَعَىٰ لَهَا سَعْيَهَا وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَأُو۟لَٰٓئِكَ كَانَ
سَعْيُهُم مَّشْكُورًا ﴿١٩﴾ كُلًّا نُّمِدُّ هَٰٓؤُلَآءِ وَهَٰٓؤُلَآءِ مِنْ
عَطَآءِ رَبِّكَ ۚ وَمَا كَانَ عَطَآءُ رَبِّكَ مَحْظُورًا ﴿٢٠﴾ ٱنظُرْ كَيْفَ
فَضَّلْنَا بَعْضَهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ ۚ وَلَلْءَاخِرَةُ أَكْبَرُ دَرَجَٰتٍ وَأَكْبَرُ
تَفْضِيلًا ﴿٢١﴾ لَّا تَجْعَلْ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ فَتَقْعُدَ مَذْمُومًا مَّخْذُولًا
﴿٢٢﴾ ۞ وَقَضَىٰ رَبُّكَ أَلَّا تَعْبُدُوٓا۟ إِلَّآ إِيَّاهُ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَٰنًا ۚ إِمَّا
يَبْلُغَنَّ عِندَكَ ٱلْكِبَرَ أَحَدُهُمَآ أَوْ كِلَاهُمَا فَلَا تَقُل لَّهُمَآ
أُفٍّ وَلَا تَنْهَرْهُمَا وَقُل لَّهُمَا قَوْلًا كَرِيمًا ﴿٢٣﴾ وَٱخْفِضْ لَهُمَا
جَنَاحَ ٱلذُّلِّ مِنَ ٱلرَّحْمَةِ وَقُل رَّبِّ ٱرْحَمْهُمَا كَمَا رَبَّيَانِى
صَغِيرًا ﴿٢٤﴾ رَّبُّكُمْ أَعْلَمُ بِمَا فِى نُفُوسِكُمْ ۚ إِن تَكُونُوا۟ صَٰلِحِينَ
فَإِنَّهُۥ كَانَ لِلْأَوَّٰبِينَ غَفُورًا ﴿٢٥﴾ وَءَاتِ ذَا ٱلْقُرْبَىٰ حَقَّهُۥ
وَٱلْمِسْكِينَ وَٱبْنَ ٱلسَّبِيلِ وَلَا تُبَذِّرْ تَبْذِيرًا ﴿٢٦﴾ إِنَّ ٱلْمُبَذِّرِينَ
كَانُوٓا۟ إِخْوَٰنَ ٱلشَّيَٰطِينِ ۖ وَكَانَ ٱلشَّيْطَٰنُ لِرَبِّهِۦ كَفُورًا ﴿٢٧﴾

(18) Wanda ya kasance yana nufin duniya ne (kawai) to za Mu gaggauto masa a cikinta abin da Muka ga dama ga wanda Muka yi nufi; sannan Mu sanya masa Jahannama, ya shige ta (a lahira) yana abin zargi, korarre (daga rahamar Allah)

(19) Wanda kuma ya nufi lahira ya kuma yi aiki irin nata dominta alhalin yana mumini, to wadannan aikinsu ya zamanto abin godewa ne (a wurin Allah)

(20) Dukkansu Muna wadata su ne da baiwar Ubangijinka; wadannan da kuma wadancan. Baiwar Ubangijinka kuwa ba ta zamo abar hanawa ba

(21) Dubi yadda Muka fifita wasunsu a kan wasu. Lalle kuwa lahira ita ta fi girman darajoji, kuma ta fi girman fifiko

(22) Kada ka hada wani abin bauta daban tare da Allah, sai ka zama abin zargi tababbe

(23) Ubangijinka kuwa Ya hukunta cewa, kada ku bauta wa (wani) sai Shi kadai, kuma ku kyautatawa iyaye. Ko dai ya zamanto dayansu ne ya manyanta tare da kai, ko kuma dukkansu, to kada ka nuna kosawarka da su, kada kuma ka daka musu tsawa; ka yi musu magana ta girmamawa

(24) Ka kuma kaskantar da kai gare su don tausayawa, ka kuma ce: "Ubangijina Ka ji kan su kamar yadda suka raine ni ina dan karami."

(25) Ubangijinku ne Mafi sanin abin da yake zukatanku. Idan kuka zamanto nagari, to lalle Shi Ya tabbata Mai gafara ne ga masu komawa gare Shi da tuba

(26) Kuma ka bai wa makusanci hakkinsa, da miskini da matafiyi, kada kuma ka yi kowane irin almubazzaranci

(27) Lalle masu almubazzaranci sun tabbata dangin shaidanu; Shaidan kuwa ya zamanto mai yawan kafirce wa Ubangijinsa ne

وَإِمَّا تُعۡرِضَنَّ عَنۡهُمُ ٱبۡتِغَآءَ رَحۡمَةٖ مِّن رَّبِّكَ تَرۡجُوهَا فَقُل لَّهُمۡ قَوۡلٗا
مَّيۡسُورٗا ٢٨ وَلَا تَجۡعَلۡ يَدَكَ مَغۡلُولَةً إِلَىٰ عُنُقِكَ وَلَا تَبۡسُطۡهَا
كُلَّ ٱلۡبَسۡطِ فَتَقۡعُدَ مَلُومٗا مَّحۡسُورًا ٢٩ إِنَّ رَبَّكَ يَبۡسُطُ ٱلرِّزۡقَ
لِمَن يَشَآءُ وَيَقۡدِرُۚ إِنَّهُۥ كَانَ بِعِبَادِهِۦ خَبِيرَۢا بَصِيرٗا ٣٠ وَلَا تَقۡتُلُوٓاْ
أَوۡلَٰدَكُمۡ خَشۡيَةَ إِمۡلَٰقٖۖ نَّحۡنُ نَرۡزُقُهُمۡ وَإِيَّاكُمۡۚ إِنَّ قَتۡلَهُمۡ كَانَ
خِطۡـًٔا كَبِيرٗا ٣١ وَلَا تَقۡرَبُواْ ٱلزِّنَىٰٓۖ إِنَّهُۥ كَانَ فَٰحِشَةٗۖ وَسَآءَ
سَبِيلٗا ٣٢ وَلَا تَقۡتُلُواْ ٱلنَّفۡسَ ٱلَّتِي حَرَّمَ ٱللَّهُ إِلَّا بِٱلۡحَقِّۗ
وَمَن قُتِلَ مَظۡلُومٗا فَقَدۡ جَعَلۡنَا لِوَلِيِّهِۦ سُلۡطَٰنٗا فَلَا يُسۡرِف فِّي
ٱلۡقَتۡلِۖ إِنَّهُۥ كَانَ مَنصُورٗا ٣٣ وَلَا تَقۡرَبُواْ مَالَ ٱلۡيَتِيمِ إِلَّا بِٱلَّتِي
هِيَ أَحۡسَنُ حَتَّىٰ يَبۡلُغَ أَشُدَّهُۥۚ وَأَوۡفُواْ بِٱلۡعَهۡدِۖ إِنَّ ٱلۡعَهۡدَ كَانَ
مَسۡـُٔولٗا ٣٤ وَأَوۡفُواْ ٱلۡكَيۡلَ إِذَا كِلۡتُمۡ وَزِنُواْ بِٱلۡقِسۡطَاسِ ٱلۡمُسۡتَقِيمِۚ
ذَٰلِكَ خَيۡرٞ وَأَحۡسَنُ تَأۡوِيلٗا ٣٥ وَلَا تَقۡفُ مَا لَيۡسَ لَكَ بِهِۦ عِلۡمٌۚ إِنَّ
ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡبَصَرَ وَٱلۡفُؤَادَ كُلُّ أُوْلَٰٓئِكَ كَانَ عَنۡهُ مَسۡـُٔولٗا ٣٦
وَلَا تَمۡشِ فِي ٱلۡأَرۡضِ مَرَحًاۖ إِنَّكَ لَن تَخۡرِقَ ٱلۡأَرۡضَ وَلَن تَبۡلُغَ
ٱلۡجِبَالَ طُولٗا ٣٧ كُلُّ ذَٰلِكَ كَانَ سَيِّئُهُۥ عِندَ رَبِّكَ مَكۡرُوهٗا ٣٨

(28) Idan kuwa ka kau da kanka daga gare su don neman wata rahama daga Ubangijinka da kake sa ran samun ta[1], to sai ka yi musu magana mai daɗi

(29) Kada kuma ka ƙuƙunce hannunka a wuyanka (ka ƙi yin kyauta), kada kuma ka shimfiɗa shi gaba ɗaya (watau ka saki komai), sai ka wayi gari abin zargi (saboda rowa), mai nadama (saboda almubazaranci)

(30) Lalle Ubangijinka Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, kuma Yana ƙuntatawa (ga wanda Ya ga dama). Lalle Shi Ya tabbata Masani ne, Mai ganin bayinsa

(31) Kada kuma ku kashe 'ya'yayenku don tsoron talauci: Mu ne Muke arzuta su har ma da ku. Lalle kashe su kuskure ne babba

(32) Kuma kada ku kusanci zina; lalle ita (zina) ta kasance mugun aiki ne, kuma hanya ce wadda ta munana

(33) Kuma kada ku kashe ran da Allah Ya haramta (kashewa) sai da haƙƙi. Wanda aka kashe ta hanyar zalunci, to lalle Mun bai wa magajinsa dama (ta ramuwa)[2], to (amma) kada ya wuce gona da iri wajen kisa; lalle shi ya zamanto abin dafa wa baya ne

(34) Kuma kada ku kusanci dukiyar maraya sai dai ta (hanya) wadda take mafi kyau[3], har sai ya kawo ƙarfi. Kuma ku cika alƙawari; lalle alƙawari ya kasance abin tambaya ne (a lahira)

(35) Kuma ku cika mudu idan kuka yi awo, kuma ku auna nauyi da ma'auni na adalci. Wannan (shi ya fi) alheri ya kuma fi kyakkyawan ƙarshe

(36) Kada kuma ka dinga bibiyar abin da ba ka da ilimi a kansa. Lalle ji da gani da kuma tunani duk waɗannan sun zama abin tambaya ne game da su

(37) Kada kuma ka yi tafiya a bayan ƙasa kana mai girman kai; lalle kai ba za ka tsaga ƙasa ba (don ƙasaita) kuma ba za ka kai tsawon duwatsu ba

(38) Duk waɗancan abubuwa mummunansu a wurin Ubangijinka abin ƙi ne

(1) Watau idan masu neman taimako a wurinsa suka zo ba ya da shi, shi ma yana jiran Allah ya hore masa.

(2) Watau ta hanyar shari'a.

(3) Watau ta hanyar yi masa kasuwanci da ita.

ذَٰلِكَ مِمَّآ أَوۡحَىٰٓ إِلَيۡكَ رَبُّكَ مِنَ ٱلۡحِكۡمَةِۗ وَلَا تَجۡعَلۡ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا
ءَاخَرَ فَتُلۡقَىٰ فِي جَهَنَّمَ مَلُومٗا مَّدۡحُورًا ٣٩ أَفَأَصۡفَىٰكُمۡ رَبُّكُم
بِٱلۡبَنِينَ وَٱتَّخَذَ مِنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ إِنَٰثًاۚ إِنَّكُمۡ لَتَقُولُونَ قَوۡلًا عَظِيمٗا ٤٠
وَلَقَدۡ صَرَّفۡنَا فِي هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ لِيَذَّكَّرُواْ وَمَا يَزِيدُهُمۡ إِلَّا نُفُورٗا ٤١
قُل لَّوۡ كَانَ مَعَهُۥٓ ءَالِهَةٞ كَمَا يَقُولُونَ إِذٗا لَّٱبۡتَغَوۡاْ إِلَىٰ ذِي ٱلۡعَرۡشِ سَبِيلٗا
٤٢ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يَقُولُونَ عُلُوّٗا كَبِيرٗا ٤٣ تُسَبِّحُ لَهُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ
ٱلسَّبۡعُ وَٱلۡأَرۡضُ وَمَن فِيهِنَّۚ وَإِن مِّن شَيۡءٍ إِلَّا يُسَبِّحُ بِحَمۡدِهِۦ وَلَٰكِن
لَّا تَفۡقَهُونَ تَسۡبِيحَهُمۡۚ إِنَّهُۥ كَانَ حَلِيمًا غَفُورٗا ٤٤ وَإِذَا قَرَأۡتَ
ٱلۡقُرۡءَانَ جَعَلۡنَا بَيۡنَكَ وَبَيۡنَ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ حِجَابٗا
مَّسۡتُورٗا ٤٥ وَجَعَلۡنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ أَكِنَّةً أَن يَفۡقَهُوهُ وَفِيٓ ءَاذَانِهِمۡ
وَقۡرٗاۚ وَإِذَا ذَكَرۡتَ رَبَّكَ فِي ٱلۡقُرۡءَانِ وَحۡدَهُۥ وَلَّوۡاْ عَلَىٰٓ أَدۡبَٰرِهِمۡ نُفُورٗا ٤٦
نَّحۡنُ أَعۡلَمُ بِمَا يَسۡتَمِعُونَ بِهِۦٓ إِذۡ يَسۡتَمِعُونَ إِلَيۡكَ وَإِذۡ هُمۡ نَجۡوَىٰٓ
إِذۡ يَقُولُ ٱلظَّٰلِمُونَ إِن تَتَّبِعُونَ إِلَّا رَجُلٗا مَّسۡحُورًا ٤٧ ٱنظُرۡ
كَيۡفَ ضَرَبُواْ لَكَ ٱلۡأَمۡثَالَ فَضَلُّواْ فَلَا يَسۡتَطِيعُونَ سَبِيلٗا ٤٨
وَقَالُوٓاْ أَءِذَا كُنَّا عِظَٰمٗا وَرُفَٰتًا أَءِنَّا لَمَبۡعُوثُونَ خَلۡقٗا جَدِيدٗا ٤٩

(39) Wannan yana daga cikin abin da Ubangijinka Ya yiwo maka wahayi da shi na hikima. Kada kuma ka sanya wani abin bauta tare da Allah, sai a jefa ka a cikin Jahannama kana abin zargi, korarre (daga rahama)

(40) Shin yanzu kuwa Ubangijinku Ya zaɓar muku 'ya'ya maza ne (Shi) kuwa Ya ɗauki ('ya'ya) mata daga mala'iku? Lalle ku tabbas kuna faɗar babbar magana

(41) Haƙiƙa kuma Mun bayyana (hujjoji) a cikin wannan Alƙur'ani don su wa'azantu, (amma) kuma ba abin da yake ƙara musu sai nesanta (daga gaskiya)

(42) Ka ce (da su): "Da dai akwai wasu alloli tare da shi (Allah), kamar yadda suke da'awa, to kuwa da sun nemi hanyar (yin hamayya) da Mai Al'arshi (watau Allah)[1]."

(43) Tsarki ya tabbata gare Shi, kuma Ya ɗaukaka ɗaukaka mai girma game da abin da suke faɗa

(44) Sammai bakwai da ƙasa da abin da yake cikinsu (duka) suna tsarkake Shi. Ba wani abu wanda ba ya tasbihi tare da gode masa, sai dai ba kwa fahimtar tasbihinsu. Lalle Shi Ya kasance Mai yawan haƙuri ne, Mai yawan gafara

(45) Idan ka karanta Alƙur'ani Mukan sanya shamaki mai karewa tsakaninka da waɗanda ba sa imani da lahira

(46) Kuma Mukan sanya marufi a kan zukatansu don kada su fahimce shi (Alƙur'anin); a cikin kunnuwansu kuma (Mukan sanya) wani nauyi. Idan kuma ka ambaci Ubangijinka Shi kaɗai a cikin Alƙur'ani sai su ba da baya suna masu bazama

(47) Mu Muka fi kowa sanin irin yadda suke sauraren sa (Alƙur'ani), yayin da suke sauraren ka (kana karanta shi), da kuma sanda suke tattaunawa, yayin da azzalumai suke cewa: "Ai ba wanda kuke bi face wani sihirtaccen mutum."

(48) Duba ka ga yadda suka yi ta ba ka sifofi (iri-iri)[2], sai suka ɓace, ba ko za su sami damar (gane) hanya ba

(49) Kuma suka ce: "Yanzu kuwa idan muka zama ƙasusuwa kuma rududdugaggu, anya kuwa za a tashe mu a sabuwar halitta?"

(1) A wata fassarar: Da su ma sun riƙa neman kusanci ne ga Allah ta hanyar yi masa ɗa'a da bauta masa.

(2) Watau ko su ce masa mawaƙi ko mai sihiri ko boka ko mai taɓin hankali.

* قُلْ كُونُوا۟ حِجَارَةً أَوْ حَدِيدًا ﴿٥٠﴾ أَوْ خَلْقًا مِّمَّا يَكْبُرُ فِى
صُدُورِكُمْ ۚ فَسَيَقُولُونَ مَن يُعِيدُنَا ۖ قُلِ ٱلَّذِى فَطَرَكُمْ أَوَّلَ مَرَّةٍ ۚ
فَسَيُنْغِضُونَ إِلَيْكَ رُءُوسَهُمْ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هُوَ ۖ قُلْ عَسَىٰٓ أَن
يَكُونَ قَرِيبًا ﴿٥١﴾ يَوْمَ يَدْعُوكُمْ فَتَسْتَجِيبُونَ بِحَمْدِهِۦ وَتَظُنُّونَ
إِن لَّبِثْتُمْ إِلَّا قَلِيلًا ﴿٥٢﴾ وَقُل لِّعِبَادِى يَقُولُوا۟ ٱلَّتِى هِىَ أَحْسَنُ ۚ
إِنَّ ٱلشَّيْطَٰنَ يَنزَغُ بَيْنَهُمْ ۚ إِنَّ ٱلشَّيْطَٰنَ كَانَ لِلْإِنسَٰنِ عَدُوًّا
مُّبِينًا ﴿٥٣﴾ رَّبُّكُمْ أَعْلَمُ بِكُمْ ۖ إِن يَشَأْ يَرْحَمْكُمْ أَوْ إِن يَشَأْ
يُعَذِّبْكُمْ ۚ وَمَآ أَرْسَلْنَٰكَ عَلَيْهِمْ وَكِيلًا ﴿٥٤﴾ وَرَبُّكَ أَعْلَمُ
بِمَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۗ وَلَقَدْ فَضَّلْنَا بَعْضَ ٱلنَّبِيِّۦنَ عَلَىٰ
بَعْضٍ ۖ وَءَاتَيْنَا دَاوُۥدَ زَبُورًا ﴿٥٥﴾ قُلِ ٱدْعُوا۟ ٱلَّذِينَ زَعَمْتُم مِّن
دُونِهِۦ فَلَا يَمْلِكُونَ كَشْفَ ٱلضُّرِّ عَنكُمْ وَلَا تَحْوِيلًا ﴿٥٦﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ
ٱلَّذِينَ يَدْعُونَ يَبْتَغُونَ إِلَىٰ رَبِّهِمُ ٱلْوَسِيلَةَ أَيُّهُمْ أَقْرَبُ
وَيَرْجُونَ رَحْمَتَهُۥ وَيَخَافُونَ عَذَابَهُۥٓ ۚ إِنَّ عَذَابَ رَبِّكَ كَانَ
مَحْذُورًا ﴿٥٧﴾ وَإِن مِّن قَرْيَةٍ إِلَّا نَحْنُ مُهْلِكُوهَا قَبْلَ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ
أَوْ مُعَذِّبُوهَا عَذَابًا شَدِيدًا ۚ كَانَ ذَٰلِكَ فِى ٱلْكِتَٰبِ مَسْطُورًا ﴿٥٨﴾

(50) Ka ce (da su): "Ku zama dutse ko ƙarfe!(51) "Ko kuma duk wata halitta da take da girma a ranku (lalle za a tashe ku)." Sannan za su ce: "To wane ne zai dawo da mu?" Ka ce (da su): "Wanda ya halicce ku tun farko." Sannan za su girgiza maka kawunansu su kuma ce: "To yaushe ne shi (wannan al'amari zai kasance)?" Ka ce (da su): "Mai yiwuwa ne ya faru ba da daɗewa ba

(52) "Ranar da zai kira ku sai ku amsa tare da gode masa kuma ku riƙa tsammanin ba ku zauna (a bayan ƙasa ba) sai ɗan lokaci ƙanƙa

ni."

(53) Ka kuma ce da bayina su faɗi (magana) wadda ita ce ta fi kyau. Lalle Shaiɗan yana ɓata tsakaninsu. Lalle Shaiɗan ya tabbata maƙiyi ne mai bayyana (ƙiyayya) ga mutum

(54) Ubangijinku (Shi) Ya fi sanin ku; in Ya ga dama sai Ya ji ƙan ku ko kuma in Ya ga dama sai Ya azabtar da ku. Ba Mu kuwa aiko ka ba don ka zama wakili a kansu

(55) Ubangijinka kuma (Shi ne) Mafi sanin abin da yake cikin sammai da ƙasa. Haƙiƙa kuma Mun fifita wasu annabawa a kan wasu; Muka kuma bai wa Dawuda (littafin) Zabura

(56) Ka ce (da su): "Ku kirawo waɗanda kuka riya (cewa su ne iyayen gijinku) ba Shi ba, to ba su da ikon yaye muku cuta ko juyar da ita."

(57) Waɗancan da suke bauta wa[1], su ma suna neman hanya ne zuwa ga Ubangijinsu, a cikinsu wa zai fi kusanci? Suna kuma ƙaunar rahamarsa, kuma suna tsoron azabarsa. Lalle azabar Ubangijinka ta kasance abar tsoro ce

(58) Kuma ba wata alƙarya[2]sai Mu ne masu halaka ta tun kafin ranar alƙiyama, ko kuma Masu azabtar da ita azaba mai tsanani. Wannan ya tabbata a rubuce cikin Littafi[3]

(1) Watau kamar mala'iku ko annabawa ko salihan bayi.

(2) Watau waɗanda za su ƙaryata manzannin Allah, su riƙa aikata manyan laifuka.

(3) Watau litttafin Lauhul Mahfuzu.

وَمَا مَنَعَنَآ أَن نُّرۡسِلَ بِٱلۡأٓيَٰتِ إِلَّآ أَن كَذَّبَ بِهَا ٱلۡأَوَّلُونَۚ وَءَاتَيۡنَا ثَمُودَ ٱلنَّاقَةَ مُبۡصِرَةٗ فَظَلَمُواْ بِهَاۚ وَمَا نُرۡسِلُ بِٱلۡأٓيَٰتِ إِلَّا تَخۡوِيفٗا ٥٩ وَإِذۡ قُلۡنَا لَكَ إِنَّ رَبَّكَ أَحَاطَ بِٱلنَّاسِۚ وَمَا جَعَلۡنَا ٱلرُّءۡيَا ٱلَّتِيٓ أَرَيۡنَٰكَ إِلَّا فِتۡنَةٗ لِّلنَّاسِ وَٱلشَّجَرَةَ ٱلۡمَلۡعُونَةَ فِي ٱلۡقُرۡءَانِۚ وَنُخَوِّفُهُمۡ فَمَا يَزِيدُهُمۡ إِلَّا طُغۡيَٰنٗا كَبِيرٗا ٦٠ وَإِذۡ قُلۡنَا لِلۡمَلَٰٓئِكَةِ ٱسۡجُدُواْ لِأٓدَمَ فَسَجَدُوٓاْ إِلَّآ إِبۡلِيسَ قَالَ ءَأَسۡجُدُ لِمَنۡ خَلَقۡتَ طِينٗا ٦١ قَالَ أَرَءَيۡتَكَ هَٰذَا ٱلَّذِي كَرَّمۡتَ عَلَيَّ لَئِنۡ أَخَّرۡتَنِ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ لَأَحۡتَنِكَنَّ ذُرِّيَّتَهُۥٓ إِلَّا قَلِيلٗا ٦٢ قَالَ ٱذۡهَبۡ فَمَن تَبِعَكَ مِنۡهُمۡ فَإِنَّ جَهَنَّمَ جَزَآؤُكُمۡ جَزَآءٗ مَّوۡفُورٗا ٦٣ وَٱسۡتَفۡزِزۡ مَنِ ٱسۡتَطَعۡتَ مِنۡهُم بِصَوۡتِكَ وَأَجۡلِبۡ عَلَيۡهِم بِخَيۡلِكَ وَرَجِلِكَ وَشَارِكۡهُمۡ فِي ٱلۡأَمۡوَٰلِ وَٱلۡأَوۡلَٰدِ وَعِدۡهُمۡۚ وَمَا يَعِدُهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ إِلَّا غُرُورًا ٦٤ إِنَّ عِبَادِي لَيۡسَ لَكَ عَلَيۡهِمۡ سُلۡطَٰنٞۚ وَكَفَىٰ بِرَبِّكَ وَكِيلٗا ٦٥ رَّبُّكُمُ ٱلَّذِي يُزۡجِي لَكُمُ ٱلۡفُلۡكَ فِي ٱلۡبَحۡرِ لِتَبۡتَغُواْ مِن فَضۡلِهِۦٓۚ إِنَّهُۥ كَانَ بِكُمۡ رَحِيمٗا ٦٦

(59) Kuma ba abin da ya hana Mu aiko da ayoyi sai don (al'ummu) na farko sun ƙaryata su; Muka kuma bai wa Samudawa taguwa (don ta zama aya) bayyananniya, sai suka butulce mata. Ba Ma kuwa aiko da ayoyi sai don tsoratarwa

(60) (Ka tuna) kuma lokacin da Muka ce da kai: "Lalle Ubangijinka Ya kewaye mutane (da ikonsa)." Ba Mu kuwa sanya abin da Muka nuna maka ido-da-ido ba (lokacin Mi'iraji) sai don jarraba ga mutane, da kuma la'ananniyar bishiyar nan (da aka ambata) a cikin Alƙur'ani.

Muna kuwa tsoratar da su ne, amma ba abin da yake ƙara musu sai ɗagawa mai girma

(61) Kuma (ka tuna) lokacin da Muka ce da mala'iku: "Ku yi sujjada ga Adamu." Sai suka yi sujjadar in ban da Iblis da ya ce: "Yanzu na yi sujjada ga wanda Ka halitta da taɓo?"

(62) Ya ce: "Ka gan Ka, wannan da Ka fifita shi a kaina, tabbas idan Ka jinkirta min har zuwa ranar alƙiyama to lalle zan karkatar da zuriyarsa, sai dai kaɗan (daga cikinsu)."

(63) (Allah) Ya ce: "Je ka (an jinkirta maka ɗin), sai dai (duk) wanda ya bi ka daga cikinsu to lalle Jahannama ce sakamakonku, wanda yake sakamako ne cikakke

(64) "Ka kuma yi wasa da hankalin wanda ka sami dama daga cikinsu da muryarka ka kuma jawo su da rundunarka mahaya da na ƙasa; ka kuma yi tarayya da su cikin dukiyoyi da 'ya'yaye; ka kuma yi musu alƙawari." Shaiɗan kuwa ba wani alƙawari da yake yi musu sai na ruɗi

(65) "Lalle bayina ba ka da iko a kansu." Kuma Ubangijinka Ya isa zama Wakili

(66) Ubangijinku Shi ne wanda Yake tafiyar da jirgi a kan kogi don ku nemi falalarsa. Lalle Shi Ya kasance Mai rahama ne a gare ku

وَإِذَا مَسَّكُمُ ٱلضُّرُّ فِى ٱلْبَحْرِ ضَلَّ مَن تَدْعُونَ إِلَّآ إِيَّاهُ ۖ فَلَمَّا
نَجَّىٰكُمْ إِلَى ٱلْبَرِّ أَعْرَضْتُمْ ۚ وَكَانَ ٱلْإِنسَٰنُ كَفُورًا ﴿٦٧﴾ أَفَأَمِنتُمْ
أَن يَخْسِفَ بِكُمْ جَانِبَ ٱلْبَرِّ أَوْ يُرْسِلَ عَلَيْكُمْ حَاصِبًا ثُمَّ
لَا تَجِدُوا۟ لَكُمْ وَكِيلًا ﴿٦٨﴾ أَمْ أَمِنتُمْ أَن يُعِيدَكُمْ فِيهِ تَارَةً
أُخْرَىٰ فَيُرْسِلَ عَلَيْكُمْ قَاصِفًا مِّنَ ٱلرِّيحِ فَيُغْرِقَكُم بِمَا كَفَرْتُمْ
ثُمَّ لَا تَجِدُوا۟ لَكُمْ عَلَيْنَا بِهِۦ تَبِيعًا ﴿٦٩﴾ * وَلَقَدْ كَرَّمْنَا بَنِىٓ
ءَادَمَ وَحَمَلْنَٰهُمْ فِى ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ وَرَزَقْنَٰهُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ
وَفَضَّلْنَٰهُمْ عَلَىٰ كَثِيرٍ مِّمَّنْ خَلَقْنَا تَفْضِيلًا ﴿٧٠﴾ يَوْمَ نَدْعُوا۟
كُلَّ أُنَاسٍۭ بِإِمَٰمِهِمْ ۖ فَمَنْ أُوتِىَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ فَأُو۟لَٰٓئِكَ
يَقْرَءُونَ كِتَٰبَهُمْ وَلَا يُظْلَمُونَ فَتِيلًا ﴿٧١﴾ وَمَن كَانَ
فِى هَٰذِهِۦٓ أَعْمَىٰ فَهُوَ فِى ٱلْءَاخِرَةِ أَعْمَىٰ وَأَضَلُّ سَبِيلًا ﴿٧٢﴾ وَإِن
كَادُوا۟ لَيَفْتِنُونَكَ عَنِ ٱلَّذِىٓ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ لِتَفْتَرِىَ
عَلَيْنَا غَيْرَهُۥ ۖ وَإِذًا لَّٱتَّخَذُوكَ خَلِيلًا ﴿٧٣﴾ وَلَوْلَآ أَن ثَبَّتْنَٰكَ
لَقَدْ كِدتَّ تَرْكَنُ إِلَيْهِمْ شَيْـًٔا قَلِيلًا ﴿٧٤﴾ إِذًا لَّأَذَقْنَٰكَ ضِعْفَ
ٱلْحَيَوٰةِ وَضِعْفَ ٱلْمَمَاتِ ثُمَّ لَا تَجِدُ لَكَ عَلَيْنَا نَصِيرًا ﴿٧٥﴾

(67) Idan kuma bala'i ya same ku a cikin kogi sai duk waɗanda kuke kira su ɓace (muku) sai Shi kawai; sannan lokacin da Ya tserar da ku zuwa sarari sai kuka bijire. Kai mutum ya tabbata butulu!
(68) Yanzu kun amince da cewa (Allah) ba zai rufto muku da wani ɓangare na tudu ba, ko kuma Ya aiko muku da jifa ta manya-manyan tsakuwoyi, sannan ba za ku sami wani mai tsaro ba?
(69) Ko kuma kun amince cewa ba zai mai da ku cikinsa ba (kogin) a karo na biyu, sai Ya aiko muku da ƙaƙƙarfar iska, sai Ya nutsar da ku saboda kafircewar da kuka yi, sannan kuma ba za ku sami wani mai nema muku haƙƙinku ba a wajenmu saboda (halakarwar da Muka yi muku)?
(70) Haƙiƙa Mun girmama 'yan'adam, Muka kuma ɗauke su (kan ababen hawa) na sarari da na ruwa, Muka kuma arzuta su daga tsarkakan (abubuwa) kuma Muka fifita su a kan wasu da yawa daga abin da Muka halitta nesa ba kusa ba
(71) Ranar da za Mu kirawo kowanne (jinsin) mutane da shugabansu, sannan wanda aka bai wa littafinsa a hannunsa na dama to waɗannan za su karanta littafinsu, sannan ba za a zalunce su ko da gwargwadon zaren ƙwallon dabino ne ba
(72) To wanda kuwa ya zamanto makaho[1] a wannan (duniya), to shi a lahira ma makaho ne kuma mafi ɓacewa daga hanyar (gaskiya)
(73) Ba shakka kuwa sun kusa su fitine ka game da abin da Muka yi maka wahayinsa don ka ƙaga mana waninsa; da kuwa haka ta faru, to da lalle sun ɗauke ka masoyi
(74) Ba don kuwa Mun tabbatar da kai (a kan umarninmu) ba, haƙiƙa da saura ƙiris ka ɗan karkata gare su
(75) To da lalle kuwa Mun ɗandana maka ninkin (azabar) rayuwa da kuma ninkin (azabar) mutuwa, sannan ba za ka samu wani mai taimakon ka a kanmu ba

(1) Watau ya ƙi ganin gaskiya ya bi ta.

وَإِن كَادُوا۟ لَيَسْتَفِزُّونَكَ مِنَ ٱلْأَرْضِ لِيُخْرِجُوكَ مِنْهَا وَإِذًا لَّا يَلْبَثُونَ خِلَٰفَكَ إِلَّا قَلِيلًا ﴿٧٦﴾ سُنَّةَ مَن قَدْ أَرْسَلْنَا قَبْلَكَ مِن رُّسُلِنَا وَلَا تَجِدُ لِسُنَّتِنَا تَحْوِيلًا ﴿٧٧﴾ أَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ لِدُلُوكِ ٱلشَّمْسِ إِلَىٰ غَسَقِ ٱلَّيْلِ وَقُرْءَانَ ٱلْفَجْرِ إِنَّ قُرْءَانَ ٱلْفَجْرِ كَانَ مَشْهُودًا ﴿٧٨﴾ وَمِنَ ٱلَّيْلِ فَتَهَجَّدْ بِهِۦ نَافِلَةً لَّكَ عَسَىٰٓ أَن يَبْعَثَكَ رَبُّكَ مَقَامًا مَّحْمُودًا ﴿٧٩﴾ وَقُل رَّبِّ أَدْخِلْنِى مُدْخَلَ صِدْقٍ وَأَخْرِجْنِى مُخْرَجَ صِدْقٍ وَٱجْعَل لِّى مِن لَّدُنكَ سُلْطَٰنًا نَّصِيرًا ﴿٨٠﴾ وَقُلْ جَآءَ ٱلْحَقُّ وَزَهَقَ ٱلْبَٰطِلُ ۚ إِنَّ ٱلْبَٰطِلَ كَانَ زَهُوقًا ﴿٨١﴾ وَنُنَزِّلُ مِنَ ٱلْقُرْءَانِ مَا هُوَ شِفَآءٌ وَرَحْمَةٌ لِّلْمُؤْمِنِينَ وَلَا يَزِيدُ ٱلظَّٰلِمِينَ إِلَّا خَسَارًا ﴿٨٢﴾ وَإِذَآ أَنْعَمْنَا عَلَى ٱلْإِنسَٰنِ أَعْرَضَ وَنَـَٔا بِجَانِبِهِۦ وَإِذَا مَسَّهُ ٱلشَّرُّ كَانَ يَـُٔوسًا ﴿٨٣﴾ قُلْ كُلٌّ يَعْمَلُ عَلَىٰ شَاكِلَتِهِۦ ۖ فَرَبُّكُمْ أَعْلَمُ بِمَنْ هُوَ أَهْدَىٰ سَبِيلًا ﴿٨٤﴾ وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلرُّوحِ ۖ قُلِ ٱلرُّوحُ مِنْ أَمْرِ رَبِّى وَمَآ أُوتِيتُم مِّنَ ٱلْعِلْمِ إِلَّا قَلِيلًا ﴿٨٥﴾ وَلَئِن شِئْنَا لَنَذْهَبَنَّ بِٱلَّذِىٓ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ ثُمَّ لَا تَجِدُ لَكَ بِهِۦ عَلَيْنَا وَكِيلًا ﴿٨٦﴾

(76) Ba shakka sun kusa su tunzura ka daga ƙasar (ta Makka) don su fitar da kai daga cikinta; da kuwa sun aikata haka to da ba za su zauna (a cikinta) ba bayanka sai ɗan lokaci ƙanƙani[1]

(77) (Wannan ita ce) irin al'adar waɗanda Muka aiko gabaninka daga manzanninmu; ba kuwa za ka sami canji a al'adarmu ba

(78) Ka tsayar da salla lokacin zawalin rana zuwa duhun dare[2], da kuma karatun sallar Asuba. Lalle (lokacin) karatun sallar asuba ya kasance lokacin halartar (mala'iku)

(79) Da daddare kuwa sai ka yi tsayuwar dare da shi (Alƙur'anin) ƙarin (daraja) ne gare ka, tare da ƙaunar Ubangijinka ya tashe ka a matsayin sha-yabo (watau matsayin mai ceto)

(80) Kuma ka ce: "Ubangijina Ka shigar da ni mashiga ta gaskiya, kuma Ka fitar da ni mafita ta gaskiya, kuma Ka ba ni wata hujja mai taimakawa daga gare ka."

(81) Kuma ka ce: "Gaskiya ta zo, ɓarna kuma ta watse. Lalle da ma can ita ɓarna ai watsattsiya ce."

(82) Kuma daga Alƙur'ani Muna saukar da abin da yake shi waraka ne da kuma rahama ga muminai; ba kuma zai ƙara azzalumai (da komai) ba sai taɓewa

(83) Kuma idan Muka yi wa mutum ni'ima sai ya bijire ya kuma juya kwiɓinsa; idan kuwa sharri ne ya same shi sai ya zama mai yawan yanke ƙauna

(84) Ka ce: "Kowa ya yi aiki bisa hanyarsa sai dai Ubangijinku (Shi ne) Mafi sanin wanda ya fi shiriya a kan madaidaiciyar hanya."

(85) Suna kuma tambayar ka game da ruhi. Ka ce da su: "Shi ruhi yana daga al'amarin Ubangijina, ba abin da aka ba ku na ilimi sai ɗan kaɗan."

(86) Kuma tabbas da Mun ga dama lalle da Mun tafiyar da abin da Muka yo maka wahayi, sannan ba za ka sami wani mataimaki ba a kanmu (game) da shi

(1) To amma ba su iya korar sa ba har zuwa lokacin da Allah ya umarce shi da hijira.

(2) Wannan lokaci ya ƙunshi sallar azahar da la'asar da magriba da isha'i.

إِلَّا رَحْمَةً مِّن رَّبِّكَ ۚ إِنَّ فَضْلَهُۥ كَانَ عَلَيْكَ كَبِيرًا ﴿٨٧﴾ قُل
لَّئِنِ ٱجْتَمَعَتِ ٱلْإِنسُ وَٱلْجِنُّ عَلَىٰٓ أَن يَأْتُوا۟ بِمِثْلِ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ
لَا يَأْتُونَ بِمِثْلِهِۦ وَلَوْ كَانَ بَعْضُهُمْ لِبَعْضٍ ظَهِيرًا ﴿٨٨﴾
وَلَقَدْ صَرَّفْنَا لِلنَّاسِ فِى هَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ مِن كُلِّ مَثَلٍ فَأَبَىٰٓ أَكْثَرُ
ٱلنَّاسِ إِلَّا كُفُورًا ﴿٨٩﴾ وَقَالُوا۟ لَن نُّؤْمِنَ لَكَ حَتَّىٰ تَفْجُرَ
لَنَا مِنَ ٱلْأَرْضِ يَنۢبُوعًا ﴿٩٠﴾ أَوْ تَكُونَ لَكَ جَنَّةٌ مِّن نَّخِيلٍ
وَعِنَبٍ فَتُفَجِّرَ ٱلْأَنْهَٰرَ خِلَٰلَهَا تَفْجِيرًا ﴿٩١﴾ أَوْ تُسْقِطَ ٱلسَّمَآءَ
كَمَا زَعَمْتَ عَلَيْنَا كِسَفًا أَوْ تَأْتِىَ بِٱللَّهِ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةِ
قَبِيلًا ﴿٩٢﴾ أَوْ يَكُونَ لَكَ بَيْتٌ مِّن زُخْرُفٍ أَوْ تَرْقَىٰ فِى ٱلسَّمَآءِ
وَلَن نُّؤْمِنَ لِرُقِيِّكَ حَتَّىٰ تُنَزِّلَ عَلَيْنَا كِتَٰبًا نَّقْرَؤُهُۥ ۗ قُلْ
سُبْحَانَ رَبِّى هَلْ كُنتُ إِلَّا بَشَرًا رَّسُولًا ﴿٩٣﴾ وَمَا مَنَعَ ٱلنَّاسَ
أَن يُؤْمِنُوٓا۟ إِذْ جَآءَهُمُ ٱلْهُدَىٰٓ إِلَّآ أَن قَالُوٓا۟ أَبَعَثَ ٱللَّهُ بَشَرًا
رَّسُولًا ﴿٩٤﴾ قُل لَّوْ كَانَ فِى ٱلْأَرْضِ مَلَٰٓئِكَةٌ يَمْشُونَ مُطْمَئِنِّينَ
لَنَزَّلْنَا عَلَيْهِم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ مَلَكًا رَّسُولًا ﴿٩٥﴾ قُلْ كَفَىٰ بِٱللَّهِ
شَهِيدًۢا بَيْنِى وَبَيْنَكُمْ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ بِعِبَادِهِۦ خَبِيرًۢا بَصِيرًا ﴿٩٦﴾

(87) Sai dai rahama daga Ubangijinka. Lalle falalarsa gare ka ta zamo mai girma ce
(88) Ka ce da su: "Lalle da mutane da aljannu sun haɗu kan su kawo irin wannan Alƙur'anin, to ba za su zo da irinsa ba, ko da kuwa wasu sun zamanto suna taimaka wa wasu."
(89) Kuma haƙiƙa Mun sarrafa wa mutane kowanne irin misali a cikin wannan Alƙur'ani, sai dai yawancin mutane sun ƙi (komai) sai kafircewa
(90) Suka kuma ce: "Ba za mu yi imani da kai ba har sai ka ɓuɓɓugo mana da idon ruwa daga ƙasa
(91) "Ko kuma ya zamana kana da wata gona ta dabinai da inabi, sai kuma ka ɓuɓɓugo da ƙoramu ta tsakiyarta su kwarara sosai
(92) "Ko kuma ka rufto da sama a kanmu, kamar yadda ka riya, ta faɗo yanki-yanki, ko kuma ka zo da Allah da kuma mala'iku (mu gan su) ido-da-ido!
(93) "Ko kuma ya zamana kana da wani gida na zinari, ko kuma ka hau sama, ba kuwa za mu amince da hawan naka ba har sai ka saukar mana da wani littafi da za mu karanta shi." Ka ce (da su): "Tsarki ya tabbata ga Ubangijina, ni ba kowa ba ne face mutum Manzo."
(94) Kuma babu abin da ya hana kafirai su yi imani lokacin da shiriya ta zo musu, sai cewar da suka yi: "Yanzu Allah ne zai aiko mutum a matsayin manzo?"
(95) Ka ce: "Da mala'iku ne suke tafiya a natse a bayan ƙasa, to da lalle Mun aiko musu mala'ika daga sama a matsayin manzo."
(96) Ka ce: "Allah Ya isa shaida tsakanina da ku: Lalle Shi ya zamanto Masani ne ga bayinsa, kuma Mai ganin (abin da suke aikatawa) ne."

وَمَن يَهْدِ ٱللَّهُ فَهُوَ ٱلْمُهْتَدِ ۖ وَمَن يُضْلِلْ فَلَن تَجِدَ لَهُمْ أَوْلِيَآءَ
مِن دُونِهِۦ ۖ وَنَحْشُرُهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ عَلَىٰ وُجُوهِهِمْ عُمْيًا وَبُكْمًا
وَصُمًّا ۖ مَّأْوَىٰهُمْ جَهَنَّمُ ۖ كُلَّمَا خَبَتْ زِدْنَٰهُمْ سَعِيرًا ﴿٩٧﴾
ذَٰلِكَ جَزَآؤُهُم بِأَنَّهُمْ كَفَرُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا وَقَالُوٓا۟ أَءِذَا كُنَّا عِظَٰمًا
وَرُفَٰتًا أَءِنَّا لَمَبْعُوثُونَ خَلْقًا جَدِيدًا ﴿٩٨﴾ أَوَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّ ٱللَّهَ
ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ قَادِرٌ عَلَىٰٓ أَن يَخْلُقَ مِثْلَهُمْ
وَجَعَلَ لَهُمْ أَجَلًا لَّا رَيْبَ فِيهِ ۖ فَأَبَى ٱلظَّٰلِمُونَ إِلَّا كُفُورًا ﴿٩٩﴾
قُل لَّوْ أَنتُمْ تَمْلِكُونَ خَزَآئِنَ رَحْمَةِ رَبِّىٓ إِذًا لَّأَمْسَكْتُمْ خَشْيَةَ
ٱلْإِنفَاقِ ۚ وَكَانَ ٱلْإِنسَٰنُ قَتُورًا ﴿١٠٠﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَىٰ تِسْعَ
ءَايَٰتٍۭ بَيِّنَٰتٍ ۖ فَسْـَٔلْ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ إِذْ جَآءَهُمْ فَقَالَ لَهُۥ فِرْعَوْنُ
إِنِّى لَأَظُنُّكَ يَٰمُوسَىٰ مَسْحُورًا ﴿١٠١﴾ قَالَ لَقَدْ عَلِمْتَ مَآ أَنزَلَ
هَٰٓؤُلَآءِ إِلَّا رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ بَصَآئِرَ ۖ وَإِنِّى لَأَظُنُّكَ
يَٰفِرْعَوْنُ مَثْبُورًا ﴿١٠٢﴾ فَأَرَادَ أَن يَسْتَفِزَّهُم مِّنَ ٱلْأَرْضِ
فَأَغْرَقْنَٰهُ وَمَن مَّعَهُۥ جَمِيعًا ﴿١٠٣﴾ وَقُلْنَا مِنۢ بَعْدِهِۦ لِبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ
ٱسْكُنُوا۟ ٱلْأَرْضَ فَإِذَا جَآءَ وَعْدُ ٱلْءَاخِرَةِ جِئْنَا بِكُمْ لَفِيفًا ﴿١٠٤﴾

(97) Wanda kuwa Allah Ya shiryar to shi ne shiryayye; wanda kuwa Ya ɓatar to ba za ka sami wani mai taimakon su ba in ban da Shi; za kuma Mu tashe su ranar alƙiyama a kan fuskokinsu suna makafi, kurame, bebaye; makomarsu Jahannama; duk sanda ta lafa sai Mu ƙara musu ƙunarta
(98) Wannan ne sakamakonsu saboda lalle sun kafirce wa ayoyinmu, suka kuma ce: "Yanzu idan muka zama ƙasusuwa kuma rududdugaggu, anya kuwa za a tashe mu a sabuwar halitta?"
(99) Yanzu ba sa gani cewa Allah wanda Ya halicci sammai da ƙasa Mai iko ne a kan Ya halicci irinsu? Ya kuma sanya musu wani lokaci wanda ba kokwanto a cikinsa, sai azzalumai suka ƙi (yin imani) sai kafircewa
(100) Ka ce da su: "Idan da ku ne kuka mallaki taskokin rahamar Ubangijina to lalle da kun riƙe su ƙam-ƙam don tsoron ciyarwa. Mutum kuwa ya tabbata mai tsananin rowa ne
(101) Kuma haƙiƙa Mun bai wa Musa ayoyi tara bayyanannu; to ka tambayi Banu Isra'ila lokacin da ya zo musu, sai Fir'auna ya ce da shi: "Lalle ni fa ina tsammanin kai Musa sihirtacce ne!"
(102) (Musa) ya ce: "Haƙiƙa ka sani ba wanda ya saukar da waɗannan (ayoyin) sai Ubangijin sammai da ƙasa don su zama hujjoji, kuma lalle ina tsammanin kai Fir'auna halakakke ne."
(103) Sai ya yi nufin ya girgiza su a ƙasar (ta Masar don ya fitar da su daga ciki), to sai Muka nutsar da shi da duk wanda yake tare da shi gaba ɗaya
(104) Muka kuma ce da Banu Isra'ila: "Ku zauna a ƙasar (ta Falasɗinu), to idan lokacin alƙiyama ya zo za Mu tattaro ku gaba ɗaya


وَبِٱلْحَقِّ أَنزَلْنَٰهُ وَبِٱلْحَقِّ نَزَلَ ۗ وَمَآ أَرْسَلْنَٰكَ إِلَّا مُبَشِّرًا وَنَذِيرًا ﴿١٠٥﴾
وَقُرْءَانًا فَرَقْنَٰهُ لِتَقْرَأَهُۥ عَلَى ٱلنَّاسِ عَلَىٰ مُكْثٍ وَنَزَّلْنَٰهُ تَنزِيلًا ﴿١٠٦﴾
قُلْ ءَامِنُوا۟ بِهِۦٓ أَوْ لَا تُؤْمِنُوٓا۟ ۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْعِلْمَ مِن قَبْلِهِۦٓ إِذَا يُتْلَىٰ
عَلَيْهِمْ يَخِرُّونَ لِلْأَذْقَانِ سُجَّدًا ﴿١٠٧﴾ وَيَقُولُونَ سُبْحَٰنَ رَبِّنَآ إِن كَانَ
وَعْدُ رَبِّنَا لَمَفْعُولًا ﴿١٠٨﴾ وَيَخِرُّونَ لِلْأَذْقَانِ يَبْكُونَ وَيَزِيدُهُمْ
خُشُوعًا ﴿١٠٩﴾ قُلِ ٱدْعُوا۟ ٱللَّهَ أَوِ ٱدْعُوا۟ ٱلرَّحْمَٰنَ ۖ أَيًّا مَّا تَدْعُوا۟ فَلَهُ
ٱلْأَسْمَآءُ ٱلْحُسْنَىٰ ۚ وَلَا تَجْهَرْ بِصَلَاتِكَ وَلَا تُخَافِتْ بِهَا وَٱبْتَغِ
بَيْنَ ذَٰلِكَ سَبِيلًا ﴿١١٠﴾ وَقُلِ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِى لَمْ يَتَّخِذْ وَلَدًا وَلَمْ يَكُن
لَّهُۥ شَرِيكٌ فِى ٱلْمُلْكِ وَلَمْ يَكُن لَّهُۥ وَلِىٌّ مِّنَ ٱلذُّلِّ ۖ وَكَبِّرْهُ تَكْبِيرًا ﴿١١١﴾

سُورَةُ الكَهۡفِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ عَلَىٰ عَبْدِهِ ٱلْكِتَٰبَ وَلَمْ يَجْعَل لَّهُۥ عِوَجًا ۜ
﴿١﴾ قَيِّمًا لِّيُنذِرَ بَأْسًا شَدِيدًا مِّن لَّدُنْهُ وَيُبَشِّرَ ٱلْمُؤْمِنِينَ
ٱلَّذِينَ يَعْمَلُونَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أَنَّ لَهُمْ أَجْرًا حَسَنًا ﴿٢﴾
مَّٰكِثِينَ فِيهِ أَبَدًا ﴿٣﴾ وَيُنذِرَ ٱلَّذِينَ قَالُوا۟ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدًا ﴿٤﴾

(105) Kuma da gaskiya Muka saukar da shi (Alkur'ani), kuma da gaskiya ya sauko. Ba Mu kuma aiko ka ba sai mai yin albishir, mai kuma gargadi
(106) Kuma Mun saukar da Kur'ani, Mun bayyana shi don ka karanta wa mutane shi a sannu a hankali, Mun kuma saukar da shi daki-daki
(107) Ka ce da su: "Ko ku yi imani da shi ko kada ku yi imani da shi (duk daya ne)." Lalle wadanda aka bai wa ilimi gabaninsa (Yahudu da Nasara)[1] idan ana karanta musu shi suna faduwa da fuskokinsu suna masu sujjada
(108) Suna kuma cewa: "Tsarki ya tabbata ga Ubangijinmu, lalle alkawarin Ubangijinmu tabbas ya zamanto abin aikatawa ne."
(109) Suna kuma faduwa da fuskokinsu suna kuka, Yana kuma kara musu kaskantar da kai
(110) Ka ce: "Ku kira (sunan) Allah ko ku kira (sunan) Arrahaman; kowanne kuka kira to shi Yana da sunaye ne mafiya kyau." Kada kuma ka daga muryarka da (karatun) sallarka, kada kuma ka yi shi a boye, ka nemi tsaka-tsakin wannan
(111) Kuma ka ce, "Yabo da godiya sun tabbata ga Allah wanda bai riki da ba, kuma ba Shi da wani abokin tarayya a cikin mulki, kuma ba Shi da wani mataimaki don kare masa kaskanci." Kuma ka girmama shi girmamawa ta sosai

Sura Kahf

(1) Dukkan yabo ya tabbata ga Allah wanda Ya saukar wa da Bawansa Littafi, bai kuma sanya masa wata karkata ba
(2) Daidaitacce ne, don ya yi gargadi game da azaba mai tsanani daga gare Shi (wato Allah), ya kuma yi wa muminai wadanda suke aiki nagari albishir cewa suna da lada kyakkyawa
(3) Madawwama a cikinsa har abada
(4) Ya kuma gargadi wadanda suka ce Allah Yana da da

(1) Watau mutanen kirki daga cikinsu.

مَّا لَهُم بِهِۦ مِنْ عِلْمٍ وَلَا لِءَابَآئِهِمْ ۚ كَبُرَتْ كَلِمَةً تَخْرُجُ مِنْ
أَفْوَٰهِهِمْ ۚ إِن يَقُولُونَ إِلَّا كَذِبًا ﴿٥﴾ فَلَعَلَّكَ بَٰخِعٌ نَّفْسَكَ
عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِمْ إِن لَّمْ يُؤْمِنُوا۟ بِهَٰذَا ٱلْحَدِيثِ أَسَفًا ﴿٦﴾ إِنَّا
جَعَلْنَا مَا عَلَى ٱلْأَرْضِ زِينَةً لَّهَا لِنَبْلُوَهُمْ أَيُّهُمْ أَحْسَنُ عَمَلًا
﴿٧﴾ وَإِنَّا لَجَٰعِلُونَ مَا عَلَيْهَا صَعِيدًا جُرُزًا ﴿٨﴾ أَمْ حَسِبْتَ
أَنَّ أَصْحَٰبَ ٱلْكَهْفِ وَٱلرَّقِيمِ كَانُوا۟ مِنْ ءَايَٰتِنَا عَجَبًا ﴿٩﴾
إِذْ أَوَى ٱلْفِتْيَةُ إِلَى ٱلْكَهْفِ فَقَالُوا۟ رَبَّنَآ ءَاتِنَا مِن لَّدُنكَ
رَحْمَةً وَهَيِّئْ لَنَا مِنْ أَمْرِنَا رَشَدًا ﴿١٠﴾ فَضَرَبْنَا عَلَىٰٓ ءَاذَانِهِمْ
فِى ٱلْكَهْفِ سِنِينَ عَدَدًا ﴿١١﴾ ثُمَّ بَعَثْنَٰهُمْ لِنَعْلَمَ أَىُّ
ٱلْحِزْبَيْنِ أَحْصَىٰ لِمَا لَبِثُوٓا۟ أَمَدًا ﴿١٢﴾ نَّحْنُ نَقُصُّ عَلَيْكَ نَبَأَهُم
بِٱلْحَقِّ ۚ إِنَّهُمْ فِتْيَةٌ ءَامَنُوا۟ بِرَبِّهِمْ وَزِدْنَٰهُمْ هُدًى ﴿١٣﴾
وَرَبَطْنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ إِذْ قَامُوا۟ فَقَالُوا۟ رَبُّنَا رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ لَن نَّدْعُوَا۟ مِن دُونِهِۦٓ إِلَٰهًا ۖ لَّقَدْ قُلْنَآ إِذًا شَطَطًا ﴿١٤﴾
هَٰٓؤُلَآءِ قَوْمُنَا ٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةً ۖ لَّوْلَا يَأْتُونَ عَلَيْهِم
بِسُلْطَٰنٍۭ بَيِّنٍ ۖ فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا ﴿١٥﴾

(5) Ba su da wani ilimi game da shi (wannan zance) kuma iyayensu ma ba su da (ilimi game da shi). Kalmar da take fitowa daga bakunansu ta yi girma. Ba abin da suke faɗa sai ƙarya

(6) To ko mai yiwuwa ne za ka kashe kanka da baƙin ciki, in ba su yi imani da wannan zancen ba (watau Alƙur'ani)

(7) Lalle Mu Mun sanya abin da yake bayan ƙasa ya zama ado a gare ta, don (kuma) Mu jarraba su, wane ne daga cikinsu ya fi kyakkyawan aiki?(8)Lalle kuma Mu za Mu mai da abin da yake kanta (ya zama) turɓaya ƙeƙasasshiyaeca.

(9) Shin ka yi tsammanin cewa lalle Mutanen Kogo da Raƙimu[1]sun kasance daga ayoyinmu masu ban mamaki?

(10) Lokacin da samarin nan suka fake a Kogon, sai suka ce: "Ya Ubangijinmu, Ka ba mu rahama daga gare Ka, Ka kuma tanadar mana shiriya cikin lamarinmu

(11) Sai Muka sanya (shamaki) a kan kunnuwansu (suka yi barci) shekaru masu yawa a cikin Kogon

(12) Sannan Muka tashe su don Mu san wane ne daga ƙungiyoyin nan biyu (masu saɓani game da lamarin samarin) ya fi kiyayewa da tsawon zamaninsu?

(13) Mu ne za Mu ba ka labarinsu da gaskiya. Lalle su samari ne da suka yi imani da Ubangijinsu, Muka kuwa ƙara musu shiriya

(14) Muka kuma ɗaure zukatansu lokacin da suka tsaya suka ce: "Ubangijinmu Shi ne Ubangijin sammai da ƙasa; ba za mu bauta wa wani abin bauta ba in ban da Shi; idan muka yi haka kuwa to haƙiƙa mun faɗi ƙarya

(1) An yi saɓani wajen fassara ma'anar arraƙimu. Wasu sun ce sunan dutsen da suka kasance a cikinsa ne; wasu kuma sun ce sunan allon da aka rubuta sunayensu a ciki; wasu kuma sun ce mutanen nan uku ne da suka shiga kogo dutse ya rufe da su.

وَإِذِ ٱعۡتَزَلۡتُمُوهُمۡ وَمَا يَعۡبُدُونَ إِلَّا ٱللَّهَ فَأۡوُۥٓاْ إِلَى ٱلۡكَهۡفِ
يَنشُرۡ لَكُمۡ رَبُّكُم مِّن رَّحۡمَتِهِۦ وَيُهَيِّئۡ لَكُم مِّنۡ أَمۡرِكُم مِّرۡفَقٗا
١٦ ۞ وَتَرَى ٱلشَّمۡسَ إِذَا طَلَعَت تَّزَٰوَرُ عَن كَهۡفِهِمۡ ذَاتَ
ٱلۡيَمِينِ وَإِذَا غَرَبَت تَّقۡرِضُهُمۡ ذَاتَ ٱلشِّمَالِ وَهُمۡ فِي فَجۡوَةٖ
مِّنۡهُۚ ذَٰلِكَ مِنۡ ءَايَٰتِ ٱللَّهِۗ مَن يَهۡدِ ٱللَّهُ فَهُوَ ٱلۡمُهۡتَدِۖ وَمَن
يُضۡلِلۡ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ وَلِيّٗا مُّرۡشِدٗا ١٧ وَتَحۡسَبُهُمۡ أَيۡقَاظٗا
وَهُمۡ رُقُودٞۚ وَنُقَلِّبُهُمۡ ذَاتَ ٱلۡيَمِينِ وَذَاتَ ٱلشِّمَالِۖ وَكَلۡبُهُم
بَٰسِطٞ ذِرَاعَيۡهِ بِٱلۡوَصِيدِۚ لَوِ ٱطَّلَعۡتَ عَلَيۡهِمۡ لَوَلَّيۡتَ مِنۡهُمۡ
فِرَارٗا وَلَمُلِئۡتَ مِنۡهُمۡ رُعۡبٗا ١٨ وَكَذَٰلِكَ بَعَثۡنَٰهُمۡ
لِيَتَسَآءَلُواْ بَيۡنَهُمۡۚ قَالَ قَآئِلٞ مِّنۡهُمۡ كَمۡ لَبِثۡتُمۡۖ قَالُواْ لَبِثۡنَا
يَوۡمًا أَوۡ بَعۡضَ يَوۡمٖۚ قَالُواْ رَبُّكُمۡ أَعۡلَمُ بِمَا لَبِثۡتُمۡ فَٱبۡعَثُوٓاْ
أَحَدَكُم بِوَرِقِكُمۡ هَٰذِهِۦٓ إِلَى ٱلۡمَدِينَةِ فَلۡيَنظُرۡ أَيُّهَآ أَزۡكَىٰ
طَعَامٗا فَلۡيَأۡتِكُم بِرِزۡقٖ مِّنۡهُ وَلۡيَتَلَطَّفۡ وَلَا يُشۡعِرَنَّ
بِكُمۡ أَحَدًا ١٩ إِنَّهُمۡ إِن يَظۡهَرُواْ عَلَيۡكُمۡ يَرۡجُمُوكُمۡ
أَوۡ يُعِيدُوكُمۡ فِي مِلَّتِهِمۡ وَلَن تُفۡلِحُوٓاْ إِذًا أَبَدٗا ٢٠

(16) “Tun da kun ƙaurace musu tare da abin da suke bauta wa sai Allah, to sai ku tare a kogon, Ubangijinku zai yalwata muku rahamarsa ya kuma shirya muku hanyar rayuwa mai sauƙi ga al’amuranku.”

(17) ((Sai) kuma ka ga rana idan za ta ɓullo tana kauce wa kogonsu ta ɓangaren dama, idan kuma za ta faɗi sai ta riƙa kauce musu ta ɓangaren hagu, su kuwa suna tsakiyarsa. Wannan yana daga ayoyin Allah. Wanda Allah Ya shiryar to shi ne shiryayye, wanda kuwa Ya ɓatar to ba za ka sami wani majiɓinci da zai shirye shi ba

(18) Za kuma ka zaci a farke suke alhali kuwa suna bacci ne. Muka kuma riƙa juya su ta ɓarin dama da kuma ta ɓarin hagu; karensu kuwa ya shimfiɗa ƙafafunsa na gaba a mashigar kogon. Da abin ka leƙa su ne to lalle da ka fita a guje, lalle kuma da ka cika da tsoron su

(19) Kamar haka Muka tashe su don su riƙa tambayar junansu. Wani mai tambaya daga cikinsu ya ce: “Mene ne tsawon zamanku (a nan)?” Suka ce: “Mun yi zaman yini ɗaya ne ko kuma rabin yini.” (Sannan kuma) suka ce: “Ubangijinku ne Ya fi sanin tsawon zaman da kuka yi, sai ku aiki ɗayanku da wannan kuɗin naku cikin gari, sai ya duba ya ga wanne irin abinci ne ya fi tsarki, to sai ya zo muku da abin da za ku ci da shi (kuɗin), kuma ya yi taka-tsantsan kada wani ya shaida ku

(20) “Lalle idan suka yi galaba a kanku to za su jefe ku ko kuma su mai da ku cikin addininsu, to shi ke nan ba za ku rabauta ba har abada.”

وَكَذَٰلِكَ أَعۡثَرۡنَا عَلَيۡهِمۡ لِيَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞ وَأَنَّ
ٱلسَّاعَةَ لَا رَيۡبَ فِيهَآ إِذۡ يَتَنَٰزَعُونَ بَيۡنَهُمۡ أَمۡرَهُمۡۖ فَقَالُواْ
ٱبۡنُواْ عَلَيۡهِم بُنۡيَٰنٗاۖ رَّبُّهُمۡ أَعۡلَمُ بِهِمۡۗ قَالَ ٱلَّذِينَ غَلَبُواْ عَلَىٰٓ
أَمۡرِهِمۡ لَنَتَّخِذَنَّ عَلَيۡهِم مَّسۡجِدٗا ٢١ سَيَقُولُونَ ثَلَٰثَةٞ
رَّابِعُهُمۡ كَلۡبُهُمۡ وَيَقُولُونَ خَمۡسَةٞ سَادِسُهُمۡ كَلۡبُهُمۡ
رَجۡمَۢا بِٱلۡغَيۡبِۖ وَيَقُولُونَ سَبۡعَةٞ وَثَامِنُهُمۡ كَلۡبُهُمۡۚ قُل رَّبِّيٓ
أَعۡلَمُ بِعِدَّتِهِم مَّا يَعۡلَمُهُمۡ إِلَّا قَلِيلٞۗ فَلَا تُمَارِ فِيهِمۡ إِلَّا مِرَآءٗ
ظَٰهِرٗا وَلَا تَسۡتَفۡتِ فِيهِم مِّنۡهُمۡ أَحَدٗا ٢٢ وَلَا تَقُولَنَّ لِشَايۡءٍ
إِنِّي فَاعِلٞ ذَٰلِكَ غَدًا ٢٣ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُۚ وَٱذۡكُر رَّبَّكَ
إِذَا نَسِيتَ وَقُلۡ عَسَىٰٓ أَن يَهۡدِيَنِ رَبِّي لِأَقۡرَبَ مِنۡ هَٰذَا رَشَدٗا
٢٤ وَلَبِثُواْ فِي كَهۡفِهِمۡ ثَلَٰثَ مِاْئَةٖ سِنِينَ وَٱزۡدَادُواْ تِسۡعٗا
٢٥ قُلِ ٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا لَبِثُواْۖ لَهُۥ غَيۡبُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ
أَبۡصِرۡ بِهِۦ وَأَسۡمِعۡۚ مَا لَهُم مِّن دُونِهِۦ مِن وَلِيّٖ وَلَا يُشۡرِكُ
فِي حُكۡمِهِۦٓ أَحَدٗا ٢٦ وَٱتۡلُ مَآ أُوحِيَ إِلَيۡكَ مِن كِتَابِ
رَبِّكَۖ لَا مُبَدِّلَ لِكَلِمَٰتِهِۦ وَلَن تَجِدَ مِن دُونِهِۦ مُلۡتَحَدٗا ٢٧

(21) Kamar haka kuwa Muka nuna wa (mutanen nasu) su don su san cewa lalle alƙawarin Allah gaskiya ne, kuma ita alƙiyama babu kokwanto a cikinta, kuma ka tuna lokacin da su (mutanen) suke ta jayayya a tsakaninsu game da al'amarinsu (watau samarin); sai (wasu daga cikinsu) suka ce: "Ku tayar da gini a kansu (wanda zai toshe ƙofar kogon)." Ubangijinsu Shi Ya fi sanin lamarinsu. Waɗanda suka yi rinjaye kan al'amarinsu suka ce: "Lalle tabbas za mu yi masallaci a kansu (watau a kan ƙabarinsu)[1].

(22) (Wasu) suka riƙa cewa su uku ne na huɗunsu shi ne karensu; (wasu) kuma suna cewa biyar ne na shidansu ne karensu don lalube cikin duhu; (wasu) kuma suna cewa su bakwai ne na takwas ɗinsu kuma karensu ne. Ka ce (da su): "Ubangiji Shi Ya fi sanin yawansu, ba wanda ya san lamarinsu sai 'yan kaɗan." To kada ka yi jayayya game da (al'amarinsu) sai dai a kan abin da yake a fili, kada kuma ka nemi fatawar ɗaya daga cikinsu game da su (samarin)

(23) Kada kuma ka ce da kowane abu: "Lalle zan aikata wannan gobe."

(24) Sai dai (tare da cewa): 'In sha Allah'; ka kuma ambaci Ubangijinka idan ka manta, kuma ka ce: "Ina fatan Ubangijina Ya nuna mini abin da ya fi wannan zama shiriya."

(25) Sun kuwa zauna cikin kogonsu shekara ɗari uku, suka kuma ƙara tara[2]

(26) Ka ce: "Allah ne Mafi sanin tsawon zaman da suka yi." Gaibun da yake sammai da ƙasa nasa ne. Wa ya yi gani irin nasa, wa kuma ya yi ji irin nasa (watau Allah). Ba su da wani majiɓinci in ban da Shi; ba Ya kuma tarayya da wani a cikin hukuncinsa

(27) Kuma ka karanta abin da aka yiwo maka wahayi da shi daga littafin Ubangijinka: Ba mai canja kalmominsa; ba kuma za ka sami wata mafaka ba in ba ta wurinsa ba

(1) Wannan magana ce ta masu iko a garin, ba ta masu ilimi ba. Musulunci yah ana gina masallaci a maƙabarta ko salla a kan ƙabari ko ana fuskantar sa.

(2) A lissafin shekarar shamsiyya, watau lissafi da fitowar rana da faɗuwarta shi ne 300. A lissafin ƙamariyya kuwa, watau lissafin ganin wata shi ne 309.

وَٱصۡبِرۡ نَفۡسَكَ مَعَ ٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ رَبَّهُم بِٱلۡغَدَوٰةِ وَٱلۡعَشِيِّ
يُرِيدُونَ وَجۡهَهُۥۖ وَلَا تَعۡدُ عَيۡنَاكَ عَنۡهُمۡ تُرِيدُ زِينَةَ ٱلۡحَيَوٰةِ
ٱلدُّنۡيَاۖ وَلَا تُطِعۡ مَنۡ أَغۡفَلۡنَا قَلۡبَهُۥ عَن ذِكۡرِنَا وَٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ وَكَانَ
أَمۡرُهُۥ فُرُطٗا ٢٨ وَقُلِ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّكُمۡۖ فَمَن شَآءَ فَلۡيُؤۡمِن وَمَن
شَآءَ فَلۡيَكۡفُرۡۚ إِنَّآ أَعۡتَدۡنَا لِلظَّٰلِمِينَ نَارًا أَحَاطَ بِهِمۡ سُرَادِقُهَاۚ
وَإِن يَسۡتَغِيثُواْ يُغَاثُواْ بِمَآءٖ كَٱلۡمُهۡلِ يَشۡوِي ٱلۡوُجُوهَۚ بِئۡسَ
ٱلشَّرَابُ وَسَآءَتۡ مُرۡتَفَقٗا ٢٩ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
ٱلصَّٰلِحَٰتِ إِنَّا لَا نُضِيعُ أَجۡرَ مَنۡ أَحۡسَنَ عَمَلًا ٣٠ أُوْلَٰٓئِكَ
لَهُمۡ جَنَّٰتُ عَدۡنٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهِمُ ٱلۡأَنۡهَٰرُ يُحَلَّوۡنَ فِيهَا مِنۡ أَسَاوِرَ
مِن ذَهَبٖ وَيَلۡبَسُونَ ثِيَابًا خُضۡرٗا مِّن سُندُسٖ وَإِسۡتَبۡرَقٖ مُّتَّكِـِٔينَ
فِيهَا عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِۚ نِعۡمَ ٱلثَّوَابُ وَحَسُنَتۡ مُرۡتَفَقٗا ٣١ ۞ وَٱضۡرِبۡ
لَهُم مَّثَلٗا رَّجُلَيۡنِ جَعَلۡنَا لِأَحَدِهِمَا جَنَّتَيۡنِ مِنۡ أَعۡنَٰبٖ وَحَفَفۡنَٰهُمَا
بِنَخۡلٖ وَجَعَلۡنَا بَيۡنَهُمَا زَرۡعٗا ٣٢ كِلۡتَا ٱلۡجَنَّتَيۡنِ ءَاتَتۡ أُكُلَهَا وَلَمۡ
تَظۡلِم مِّنۡهُ شَيۡـٔٗاۚ وَفَجَّرۡنَا خِلَٰلَهُمَا نَهَرٗا ٣٣ وَكَانَ لَهُۥ ثَمَرٞ فَقَالَ
لِصَٰحِبِهِۦ وَهُوَ يُحَاوِرُهُۥٓ أَنَا۠ أَكۡثَرُ مِنكَ مَالٗا وَأَعَزُّ نَفَرٗا ٣٤

(28) Ka kuma haƙurƙurtar da kanka (da zama) tare da waɗanda suke bauta wa Ubangijinsu safe da yamma suna neman yardarsa; kar kuma ka kawar da idanuwanka daga gare su kana neman adon rayuwar duniya; kada kuma ka bi wanda Muka shagaltar da zuciyarsa daga ambatonmu ya kuma bi son ransa, wanda kuma al'amarinsa ya zama a sukurkuce

(29) Kuma ka ce: "Gaskiya daga Ubangijinku take;" to wanda ya ga dama ya yi imani, wanda kuma ya ga dama sai ya kafirta. Lalle kam Mun tanadar wa azzalumai wata wuta wadda katangarta ta kewaye su. Idan kuma suka nemi taimako to za a taimake su ne da ruwa kamar tafasasshen mai da zai rƙa toye fuskoki. Tir da wannan abin shan, makoma kuma ta munana

(30) Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari tabbas Mu ba ma tozarta ladan wanda ya kyautata aiki

(31) Waɗannan suna da gidajen Aljanna na dawwama waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, ana yi musu ado a cikinsu (watau gidajen) da awarwaro na zinare, suna kuma sanya tufafi koraye na alharini mai shara-shara da mai kauri, suna kwance a kan gadaje. Madalla (da wannan) lada, wurin hutu kuma ya kyautata

(32) Ka kuma ba su misali da wasu mutane su biyu da Muka tanadar wa ɗayansu gonakai biyu na inabi, Muka kuma kewaye su da dabinai, Muka kuma sanya wasu shukoki tsakaninsu

(33) Kowace ɗaya daga gonakin ta ba da 'ya'yanta kuma ba ta rage komai daga gare su ba. Muka kuma ɓuɓɓugo da ƙorama ta tsakiyarsu

(34) Ya zamanto yana da 'ya'yan itace, sai ya ce da abokinsa yayin da yake mahawara da shi: "Ni na fi ka yawan dukiya da ƙarfin jama'a."

وَدَخَلَ جَنَّتَهُۥ وَهُوَ ظَالِمٌ لِّنَفْسِهِۦ قَالَ مَآ أَظُنُّ أَن تَبِيدَ هَٰذِهِۦٓ
أَبَدًا ﴿٣٥﴾ وَمَآ أَظُنُّ ٱلسَّاعَةَ قَآئِمَةً وَلَئِن رُّدِدتُّ إِلَىٰ رَبِّى لَأَجِدَنَّ
خَيْرًا مِّنْهَا مُنقَلَبًا ﴿٣٦﴾ قَالَ لَهُۥ صَاحِبُهُۥ وَهُوَ يُحَاوِرُهُۥٓ أَكَفَرْتَ
بِٱلَّذِى خَلَقَكَ مِن تُرَابٍ ثُمَّ مِن نُّطْفَةٍ ثُمَّ سَوَّىٰكَ رَجُلًا ﴿٣٧﴾
لَّٰكِنَّا۠ هُوَ ٱللَّهُ رَبِّى وَلَآ أُشْرِكُ بِرَبِّىٓ أَحَدًا ﴿٣٨﴾ وَلَوْلَآ إِذْ دَخَلْتَ
جَنَّتَكَ قُلْتَ مَا شَآءَ ٱللَّهُ لَا قُوَّةَ إِلَّا بِٱللَّهِ ۚ إِن تَرَنِ أَنَا۠ أَقَلَّ مِنكَ
مَالًا وَوَلَدًا ﴿٣٩﴾ فَعَسَىٰ رَبِّىٓ أَن يُؤْتِيَنِ خَيْرًا مِّن جَنَّتِكَ وَيُرْسِلَ
عَلَيْهَا حُسْبَانًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ فَتُصْبِحَ صَعِيدًا زَلَقًا ﴿٤٠﴾ أَوْ يُصْبِحَ
مَآؤُهَا غَوْرًا فَلَن تَسْتَطِيعَ لَهُۥ طَلَبًا ﴿٤١﴾ وَأُحِيطَ بِثَمَرِهِۦ
فَأَصْبَحَ يُقَلِّبُ كَفَّيْهِ عَلَىٰ مَآ أَنفَقَ فِيهَا وَهِىَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ
عُرُوشِهَا وَيَقُولُ يَٰلَيْتَنِى لَمْ أُشْرِكْ بِرَبِّىٓ أَحَدًا ﴿٤٢﴾ وَلَمْ تَكُن لَّهُۥ
فِئَةٌ يَنصُرُونَهُۥ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَمَا كَانَ مُنتَصِرًا ﴿٤٣﴾ هُنَالِكَ ٱلْوَلَٰيَةُ
لِلَّهِ ٱلْحَقِّ ۚ هُوَ خَيْرٌ ثَوَابًا وَخَيْرٌ عُقْبًا ﴿٤٤﴾ وَٱضْرِبْ لَهُم مَّثَلَ ٱلْحَيَوٰةِ
ٱلدُّنْيَا كَمَآءٍ أَنزَلْنَٰهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَٱخْتَلَطَ بِهِۦ نَبَاتُ ٱلْأَرْضِ
فَأَصْبَحَ هَشِيمًا تَذْرُوهُ ٱلرِّيَٰحُ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ مُّقْتَدِرًا ﴿٤٥﴾

(35) Ya kuma shiga gonarsa yana kuwa mai zaluntar kansa(1), ya ce: “Ba na tsammanin cewa wannan za ta ƙare har abada.”
(36) “Kuma ba na tsammanin alƙiyama za ta tashi, kuma ko da an mayar da ni wurin Ubangijina to lalle zan sami canji fiye ma da ita.”
(37) Abokinsa ya ce da shi yana mai mahawara da shi: “Yanzu ka kafirce wa Wanda Ya halicce ka daga ƙasa, sannan (kuma) daga maniyyi, sannan Ya daidaita ka (ka zama) mutum?
(38) “Sai dai ni kam Allah Shi ne Ubangijina, ba kuwa zan haɗa wani da Ubangijina ba
(39) “Kuma mai ya hana ka lokacin da ka shiga gonarka ka ce: ‘Abin da Allah Ya ga dama (shi zai kasance). Babu wani ƙarfi kuma babu dabara sai da Allah.’ Idan kana gani na na fi ka ƙarancin dukiya da ‘ya’ya
(40) “To ina fatan Ubangijina Ya ba ni fiye da gonarka, Ya kuma aiko mata (gonarka) da wani bala’i daga sama, sannan ta wayi gari ta zama ƙeƙasasshiyar ƙasa mai santsi
(41) “Ko kuma ruwanta ya zama ya ƙafe ƙarƙaf, ba ko za ka sami hanyar samo shi ba.”
(42) Aka kuwa hallaka ‘ya’yan itacen nasa, sannan ya wayi gari yana tafa hannayensa kan irin abin da ya ɓatar a kanta, ita kuwa ga ta ta zubo a kan dirkokinta, yana kuma cewa: “Kaicona, ina ma ban haɗa wani da Ubangijina ba!”
(43) Ba shi kuwa da wata ƙungiya da za ta taimake shi ban da Allah, kuma bai zamo mai taimaka wa (kansa) ba(44) A wannan lokacin ne (ya bayyana) cewa taimako na Allah ne Tabbataccen (Sarki). Shi ne Fiyayyen Mai ba da lada kuma Fiyayyen Mai kyautata ƙarshe
(45) Kuma ka ba su misalin rayuwar duniya (wadda take) kamar ruwa ne da Muka saukar da shi daga sama, sai tsirran ƙasa suka cakuɗa da shi, sannan ya zama busasshe, iska tana ɗaidaita shi. Allah kuwa Ya kasance Mai iko ne a kan komai

(1) Yana alfahari da rashin nuna godiya ga Allah.

ٱلْمَالُ وَٱلْبَنُونَ زِينَةُ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ وَٱلْبَٰقِيَٰتُ ٱلصَّٰلِحَٰتُ
خَيْرٌ عِندَ رَبِّكَ ثَوَابًا وَخَيْرٌ أَمَلًا ﴿٤٦﴾ وَيَوْمَ نُسَيِّرُ ٱلْجِبَالَ وَتَرَى
ٱلْأَرْضَ بَارِزَةً وَحَشَرْنَٰهُمْ فَلَمْ نُغَادِرْ مِنْهُمْ أَحَدًا ﴿٤٧﴾ وَعُرِضُوا۟
عَلَىٰ رَبِّكَ صَفًّا لَّقَدْ جِئْتُمُونَا كَمَا خَلَقْنَٰكُمْ أَوَّلَ مَرَّةٍۭ ۖ بَلْ زَعَمْتُمْ
أَلَّن نَّجْعَلَ لَكُم مَّوْعِدًا ﴿٤٨﴾ وَوُضِعَ ٱلْكِتَٰبُ فَتَرَى ٱلْمُجْرِمِينَ
مُشْفِقِينَ مِمَّا فِيهِ وَيَقُولُونَ يَٰوَيْلَتَنَا مَالِ هَٰذَا ٱلْكِتَٰبِ
لَا يُغَادِرُ صَغِيرَةً وَلَا كَبِيرَةً إِلَّآ أَحْصَىٰهَا ۚ وَوَجَدُوا۟ مَا عَمِلُوا۟
حَاضِرًا ۗ وَلَا يَظْلِمُ رَبُّكَ أَحَدًا ﴿٤٩﴾ وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ ٱسْجُدُوا۟
لِءَادَمَ فَسَجَدُوٓا۟ إِلَّآ إِبْلِيسَ ۖ كَانَ مِنَ ٱلْجِنِّ فَفَسَقَ عَنْ أَمْرِ رَبِّهِۦٓ ۗ
أَفَتَتَّخِذُونَهُۥ وَذُرِّيَّتَهُۥٓ أَوْلِيَآءَ مِن دُونِى وَهُمْ لَكُمْ عَدُوٌۢ ۚ
بِئْسَ لِلظَّٰلِمِينَ بَدَلًا ﴿٥٠﴾ مَّآ أَشْهَدتُّهُمْ خَلْقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ وَلَا خَلْقَ أَنفُسِهِمْ ۖ وَمَا كُنتُ مُتَّخِذَ ٱلْمُضِلِّينَ عَضُدًا
﴿٥١﴾ وَيَوْمَ يَقُولُ نَادُوا۟ شُرَكَآءِىَ ٱلَّذِينَ زَعَمْتُمْ فَدَعَوْهُمْ
فَلَمْ يَسْتَجِيبُوا۟ لَهُمْ وَجَعَلْنَا بَيْنَهُم مَّوْبِقًا ﴿٥٢﴾ وَرَءَا ٱلْمُجْرِمُونَ
ٱلنَّارَ فَظَنُّوٓا۟ أَنَّهُم مُّوَاقِعُوهَا وَلَمْ يَجِدُوا۟ عَنْهَا مَصْرِفًا ﴿٥٣﴾

(46) Dukiya da ‘ya’ya adon rayuwar duniya ne; wanzazzun ayyuka nagari kuwa su suka fi lada a wurin Ubangijinka kuma su ne buri mafi alheri

(47) Kuma ka tuna ranar da za Mu tafiyar da duwatsu kuma ka ga ƙasa a baje (ba tudu ba rafi), Mu kuma tattara su (gaba ɗaya), ba Mu bar ɗaya daga cikinsu ba

(48) Aka kuma kawo su a gaban Ubangijinka sahu-sahu (a ce da su): “Haƙiƙa kun zo mana kamar yadda tun farko Muka halicce ku. Ba ma haka ba, kun riya cewa ba za Mu sanya muku wani wa’adi ba.”

(49) Aka kuma ajiye littafin (ayyukansu), sannan sai ka ga masu laifi suna cike da tsoron abin da yake cikinsa, suna kuma cewa: “Kaiconmu, me ya sami wannan littafin, ba ya barin (aiki) ƙarami balle babba sai ya ƙididdige su. Suka kuma sami (duk) abubuwan da suka aikata an zo da su. Ubangijinka kuwa ba zai zalunci kowa ba

(50) Kuma ka tuna lokacin da Muka ce da mala’iku: “Ku yi sujjada ga Adamu”, sai suka yi sujjadar in ban da Iblis, ya kasance kuwa daga cikin aljannu, sai ya saɓa wa umarnin Ubangijinsa. Yanzu kwa riƙe shi shi da zurriyarsa masoya ba Ni ba, alhali kuwa su maƙiyanku ne? Wannan canji na azzalumai ya munana

(51) Ban halarto da su ba lokacin halittar sammai da ƙasa, ko ma halittar kawunansu, ban kuma kasance Mai rikon masu ɓatarwa mataimaka ba

(52) Kuma (ka tuna) ranar da (Allah) zai ce (da kafirai): “Ku kirawo abokan tarayyar nawa waɗanda kuka riya (cewa su ne iyayen gijinku)”, to sai suka kirawo su, sai ba su amsa musu ba, Muka kuma sanya mahallaka a tsakaninsu

(53) Masu laifi kuma suka ga wuta sai suka tabbatar da cewa lalle za su shige ta ba kuwa za su sami wata makauta ba daga gare ta

وَلَقَدْ صَرَّفْنَا فِي هَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ لِلنَّاسِ مِن كُلِّ مَثَلٍ ۚ وَكَانَ
ٱلْإِنسَٰنُ أَكْثَرَ شَيْءٍ جَدَلًا ﴿٥٤﴾ وَمَا مَنَعَ ٱلنَّاسَ أَن يُؤْمِنُوٓا۟
إِذْ جَآءَهُمُ ٱلْهُدَىٰ وَيَسْتَغْفِرُوا۟ رَبَّهُمْ إِلَّآ أَن تَأْتِيَهُمْ سُنَّةُ
ٱلْأَوَّلِينَ أَوْ يَأْتِيَهُمُ ٱلْعَذَابُ قُبُلًا ﴿٥٥﴾ وَمَا نُرْسِلُ ٱلْمُرْسَلِينَ
إِلَّا مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ ۚ وَيُجَٰدِلُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِٱلْبَٰطِلِ
لِيُدْحِضُوا۟ بِهِ ٱلْحَقَّ ۖ وَٱتَّخَذُوٓا۟ ءَايَٰتِى وَمَآ أُنذِرُوا۟ هُزُوًا ﴿٥٦﴾
وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن ذُكِّرَ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِۦ فَأَعْرَضَ عَنْهَا وَنَسِىَ
مَا قَدَّمَتْ يَدَاهُ ۚ إِنَّا جَعَلْنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ أَكِنَّةً أَن يَفْقَهُوهُ
وَفِىٓ ءَاذَانِهِمْ وَقْرًا ۖ وَإِن تَدْعُهُمْ إِلَى ٱلْهُدَىٰ فَلَن يَهْتَدُوٓا۟ إِذًا
أَبَدًا ﴿٥٧﴾ وَرَبُّكَ ٱلْغَفُورُ ذُو ٱلرَّحْمَةِ ۖ لَوْ يُؤَاخِذُهُم بِمَا كَسَبُوا۟
لَعَجَّلَ لَهُمُ ٱلْعَذَابَ ۚ بَل لَّهُم مَّوْعِدٌ لَّن يَجِدُوا۟ مِن دُونِهِۦ
مَوْئِلًا ﴿٥٨﴾ وَتِلْكَ ٱلْقُرَىٰٓ أَهْلَكْنَٰهُمْ لَمَّا ظَلَمُوا۟ وَجَعَلْنَا
لِمَهْلِكِهِم مَّوْعِدًا ﴿٥٩﴾ وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِفَتَىٰهُ لَآ أَبْرَحُ حَتَّىٰٓ
أَبْلُغَ مَجْمَعَ ٱلْبَحْرَيْنِ أَوْ أَمْضِىَ حُقُبًا ﴿٦٠﴾ فَلَمَّا بَلَغَا مَجْمَعَ
بَيْنِهِمَا نَسِيَا حُوتَهُمَا فَٱتَّخَذَ سَبِيلَهُۥ فِى ٱلْبَحْرِ سَرَبًا ﴿٦١﴾

(54) Kuma hakika Mun sassarafa kowane irin misali ga mutane a cikin wannan Alkur'anin. Mutum kuwa ya kasance wanda ya fi komai yawan musu

(55) Ba kuwa abin da ya hana mutane su yi imani lokacin da shiriya ta zo musu, su kuma nemi gafarar Ubangijinsu har sai irin abin da ya zo wa mutanen farko ya zo musu, ko kuwa azaba ta zo musu gaba-da-gaba

(56) Ba Mu kuma aiko da manzanni ba sai don su zama masu albishir mai gargadi. Su kuma wadanda suka kafirce sai su dinga jayayya da karya don su kawar da gaskiya da ita; suka kuma riki ayoyina da kuma abin da aka yi musu gargadi da shi a matsayin abin izgili

(57) Wane ne ya fi zalunci fiye da wanda aka yi masa gargadi da ayoyin Ubangijinsa sannan ya bijire musu, ya kuma manta abin da hannayensa suka gabatar (na mugun aiki). Lalle Mun sanya rufi a zukatansu don kada su fahimce shi (Alkur'ani), a cikin kunnuwansu kuma (Muka sanya) wani nauyi. Idan kuwa ka kirawo su zuwa ga shiriya to ba za su yi imani ba har abada

(58) Ubangijinka kuwa Mai yawan gafara ne Ma'abocin rahama; da Yana kama su da abin da suka aikata, to da Ya gaggauta musu azaba. A'a, (ba Ya yin haka), sai dai suna da kayyadajjen lokaci wanda ba za su sami wata makauta ba daga gare shi

(59) Kuma wadancan alkaryu Mun hallakar da su yayin da suka yi zalunci, Muka kuma sanya kayyadajjen lokaci na hallakar da su

(60) Kuma (ka tuna) lokacin da Musa ya ce da yaronsa: "Ba zan dakata da (tafiyata) ba har sai na kai mahadar kogunan nan biyu, ko kuwa in zarce har tsawon shekaru[1]."

(61) To lokacin da suka isa mahadar tasu (watau kogunan) sai suka manta da kifinsu wanda ya kama hanyarsa a cikin kogi kamar dakin karkashin kasa

(1) Daga nan har zuwa karshen aya ta 82 Allah ( ) ya ba da labarin tafiyar Annabi Musa ( ) neman ilimi wajen Annabi Khadir ( ). Yaronsa shi ne Annabi Yusha'u ( ).

فَلَمَّا جَاوَزَا قَالَ لِفَتَىٰهُ ءَاتِنَا غَدَآءَنَا لَقَدْ لَقِينَا مِن سَفَرِنَا
هَٰذَا نَصَبًا ﴿٦٢﴾ قَالَ أَرَءَيْتَ إِذْ أَوَيْنَآ إِلَى ٱلصَّخْرَةِ فَإِنِّى نَسِيتُ
ٱلْحُوتَ وَمَآ أَنسَىٰنِيهُ إِلَّا ٱلشَّيْطَٰنُ أَنْ أَذْكُرَهُۥ ۚ وَٱتَّخَذَ سَبِيلَهُۥ
فِى ٱلْبَحْرِ عَجَبًا ﴿٦٣﴾ قَالَ ذَٰلِكَ مَا كُنَّا نَبْغِ ۚ فَٱرْتَدَّا عَلَىٰٓ ءَاثَارِهِمَا
قَصَصًا ﴿٦٤﴾ فَوَجَدَا عَبْدًا مِّنْ عِبَادِنَآ ءَاتَيْنَٰهُ رَحْمَةً مِّنْ عِندِنَا
وَعَلَّمْنَٰهُ مِن لَّدُنَّا عِلْمًا ﴿٦٥﴾ قَالَ لَهُۥ مُوسَىٰ هَلْ أَتَّبِعُكَ عَلَىٰٓ أَن
تُعَلِّمَنِ مِمَّا عُلِّمْتَ رُشْدًا ﴿٦٦﴾ قَالَ إِنَّكَ لَن تَسْتَطِيعَ مَعِىَ
صَبْرًا ﴿٦٧﴾ وَكَيْفَ تَصْبِرُ عَلَىٰ مَا لَمْ تُحِطْ بِهِۦ خُبْرًا ﴿٦٨﴾ قَالَ
سَتَجِدُنِىٓ إِن شَآءَ ٱللَّهُ صَابِرًا وَلَآ أَعْصِى لَكَ أَمْرًا ﴿٦٩﴾ قَالَ
فَإِنِ ٱتَّبَعْتَنِى فَلَا تَسْـَٔلْنِى عَن شَىْءٍ حَتَّىٰٓ أُحْدِثَ لَكَ مِنْهُ ذِكْرًا
﴿٧٠﴾ فَٱنطَلَقَا حَتَّىٰٓ إِذَا رَكِبَا فِى ٱلسَّفِينَةِ خَرَقَهَا ۖ قَالَ أَخَرَقْتَهَا
لِتُغْرِقَ أَهْلَهَا لَقَدْ جِئْتَ شَيْـًٔا إِمْرًا ﴿٧١﴾ قَالَ أَلَمْ أَقُلْ إِنَّكَ
لَن تَسْتَطِيعَ مَعِىَ صَبْرًا ﴿٧٢﴾ قَالَ لَا تُؤَاخِذْنِى بِمَا نَسِيتُ وَلَا
تُرْهِقْنِى مِنْ أَمْرِى عُسْرًا ﴿٧٣﴾ فَٱنطَلَقَا حَتَّىٰٓ إِذَا لَقِيَا غُلَٰمًا فَقَتَلَهُۥ
قَالَ أَقَتَلْتَ نَفْسًا زَكِيَّةًۢ بِغَيْرِ نَفْسٍ لَّقَدْ جِئْتَ شَيْـًٔا نُّكْرًا ﴿٧٤﴾

(62) To lokacin da suka wuce (wannan wuri) sai (Musa) ya ce da yaronsa: “Kawo mana abincinmu, haƙiƙa mun haɗu da wahala cikin wannan tafiya tamu.”

(63) Sai (yaron) ya ce: “Ba ka gani ba lokacin da muka fake a daidai dutsen nan ai sai na manta da kifin, ba kuwa wani ne ya mantar da ni shi ba sai Shaiɗan, ya hana ni in tuna. Sai kuma ya kama hanyarsa cikin kogi, abin mamaki!”

(64) (Musa) ya ce: “Wannan da ma shi ne abin da muke nema”, Sai suka koma da baya suna bin sawunsu (ta inda suka fito)

(65) To sai suka sami wani bawa daga bayinmu wanda Muka bai wa rahama daga gare Mu, kuma Muka koyar da shi wani ilimi daga wajenmu

(66) Musa ya ce da shi: “Shin na iya bin ka don ka koyar da ni (wani abu) daga abin da aka koyar da kai na shiriya?”

(67) Ya ce: “Lalle ba za ka iya haƙuri da ni ba(68) “Kaƙa kuwa za ka yi haƙuri kan abin da ba ka kewaye da saninsa ba?”(69)(Musa) ya ce: “Za ka same ni mai haƙuri in sha Allahu, ba kuma zan saɓa wa umarninka ba.”

(70) Ya ce, “To idan ka bi ni kada ka tambaye ni game da kowane abu har sai na ba ka labari game da shi.”

(71) Sai suka tafi, har lokacin da suka shiga cikin jirgin ruwa, to sai ya huda shi; sai (Musa) ya ce: “Yanzu ka huda shi ne don ka nutsar da waɗanda suke cikinsa? Haƙiƙa ka zo da babban abu.”

(72) Ya ce: “Ban faɗa maka ba cewa kai ba za ka iya haƙuri da ni ba?”

(73) (Musa) ya ce: “Kada ka kama ni da abin da na manta, kada kuma ka ɗora mini abu mai wahala game da al’amarina.”

(74) Sai suka ci gaba da tafiya har dai suka gamu da wani yaro, to sai ya kashe shi, (Musa) ya ce: “Yanzu ka kashe rai tsarkakakke ba tare da (ya kashe) wani rai ba? Haƙiƙa ka zo da wani abu mummuna!”

* قَالَ أَلَمْ أَقُل لَّكَ إِنَّكَ لَن تَسْتَطِيعَ مَعِيَ صَبْرًا ﴿٧٥﴾ قَالَ إِن
سَأَلْتُكَ عَن شَيْءٍ بَعْدَهَا فَلَا تُصَٰحِبْنِي ۖ قَدْ بَلَغْتَ مِن لَّدُنِّي عُذْرًا
﴿٧٦﴾ فَٱنطَلَقَا حَتَّىٰٓ إِذَآ أَتَيَآ أَهْلَ قَرْيَةٍ ٱسْتَطْعَمَآ أَهْلَهَا فَأَبَوْا۟
أَن يُضَيِّفُوهُمَا فَوَجَدَا فِيهَا جِدَارًا يُرِيدُ أَن يَنقَضَّ فَأَقَامَهُۥ ۖ
قَالَ لَوْ شِئْتَ لَتَّخَذْتَ عَلَيْهِ أَجْرًا ﴿٧٧﴾ قَالَ هَٰذَا فِرَاقُ بَيْنِي
وَبَيْنِكَ ۚ سَأُنَبِّئُكَ بِتَأْوِيلِ مَا لَمْ تَسْتَطِع عَّلَيْهِ صَبْرًا ﴿٧٨﴾ أَمَّا
ٱلسَّفِينَةُ فَكَانَتْ لِمَسَٰكِينَ يَعْمَلُونَ فِي ٱلْبَحْرِ فَأَرَدتُّ أَنْ
أَعِيبَهَا وَكَانَ وَرَآءَهُم مَّلِكٌ يَأْخُذُ كُلَّ سَفِينَةٍ غَصْبًا ﴿٧٩﴾ وَأَمَّا
ٱلْغُلَٰمُ فَكَانَ أَبَوَاهُ مُؤْمِنَيْنِ فَخَشِينَآ أَن يُرْهِقَهُمَا طُغْيَٰنًا
وَكُفْرًا ﴿٨٠﴾ فَأَرَدْنَآ أَن يُبْدِلَهُمَا رَبُّهُمَا خَيْرًا مِّنْهُ زَكَوٰةً وَأَقْرَبَ
رُحْمًا ﴿٨١﴾ وَأَمَّا ٱلْجِدَارُ فَكَانَ لِغُلَٰمَيْنِ يَتِيمَيْنِ فِي ٱلْمَدِينَةِ
وَكَانَ تَحْتَهُۥ كَنزٌ لَّهُمَا وَكَانَ أَبُوهُمَا صَٰلِحًا فَأَرَادَ رَبُّكَ أَن
يَبْلُغَآ أَشُدَّهُمَا وَيَسْتَخْرِجَا كَنزَهُمَا رَحْمَةً مِّن رَّبِّكَ ۚ
وَمَا فَعَلْتُهُۥ عَنْ أَمْرِي ۚ ذَٰلِكَ تَأْوِيلُ مَا لَمْ تَسْطِع عَّلَيْهِ صَبْرًا ﴿٨٢﴾
وَيَسْـَٔلُونَكَ عَن ذِي ٱلْقَرْنَيْنِ ۖ قُلْ سَأَتْلُوا۟ عَلَيْكُم مِّنْهُ ذِكْرًا ﴿٨٣﴾

(75) Ya ce: “Shin ban faɗa maka cewa lalle kai ba za ka iya haƙuri da ni ba?”
(76) (Musa) ya ce: “Idan na sake tambayar ka wani abu bayansa, to kada ka tafi tare da ni; haƙiƙa ka sami (cikakken) hanzari a kaina.”
(77) Sai suka ci gaba da tafiya har suka iso ga mutanen wata alƙarya, sai suka nemi mutanen alƙaryar su ciyar da su, to sai suka ƙi su karɓi baƙuntarsu, sai suka samu wani garu a alƙaryar yana haramar rugujewa sai (Khadiru) ya tashe shi, sai (Musa) ya ce: “Da ka ga dama ai da sai ka karɓi lada a kansa.” (Watau aikin tayarwar)
(78) Ya ce: “Wannan ita ce rabuwata da kai. Zan ba ka labarin abin da ka kasa haƙuri a kansa.
(79) “To game da shi jirgin ruwan nan ya kasance na wasu miskinai ne da suke aiki a cikin kogi, to sai na yi nufin in lalata shi domin kuwa a gabansu akwai wani sarki da yake ƙwace kowane jirgin ruwa (lafiyayye)
(80) “To amma kuma game da shi yaron nan, iyayensa sun kasance muminai ne, sai muka ji tsoron kada ya afkar da su cikin shisshigi da kafirci
(81) “Sai muka yi nufin Ubangijinsu Ya musanya musu (wani ɗa) wanda ya fi tsarkaka ya kuma fi shi tausayi
(82) “To game da shi garun nan kuwa ya kasance na wasu yara ne marayu a cikin wannan birnin, a ƙarƙashinsa kuwa da akwai wata taska tasu, mahaifinsu kuma ya kasance mutumin kirki ne, to sai Ubangijinka Ya nufi su girma su cika hankalinsu su, kuma fito da taskarsu, don rahama daga Ubangijinka. Ban aikata haka ba ne da raɗin kaina. Wannan shi ne fassarar abin da ka kasa haƙuri a kansa.”
(83) SSuna kuma tambayar ka game da Zulƙarnaini[1]; ka ce (da su): “Ba da daɗewa ba zan ba ku labari a kansa.”

(1) Daga nan har zuwa aya ta 98 Allah ya ba da labarin Zulƙarnaini ne. Shi kuma wani sarki ne mumini da Allah ya ba shi ƙarfin Mulki har ya ci garuruwa masu yawa da yaƙi.

إِنَّا مَكَّنَّا لَهُۥ فِى ٱلْأَرْضِ وَءَاتَيْنَٰهُ مِن كُلِّ شَىْءٍ سَبَبًا ﴿٨٤﴾ فَأَتْبَعَ سَبَبًا
﴿٨٥﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ مَغْرِبَ ٱلشَّمْسِ وَجَدَهَا تَغْرُبُ فِى عَيْنٍ حَمِئَةٍ
وَوَجَدَ عِندَهَا قَوْمًا ۗ قُلْنَا يَٰذَا ٱلْقَرْنَيْنِ إِمَّآ أَن تُعَذِّبَ وَإِمَّآ أَن تَتَّخِذَ
فِيهِمْ حُسْنًا ﴿٨٦﴾ قَالَ أَمَّا مَن ظَلَمَ فَسَوْفَ نُعَذِّبُهُۥ ثُمَّ يُرَدُّ إِلَىٰ رَبِّهِۦ
فَيُعَذِّبُهُۥ عَذَابًا نُّكْرًا ﴿٨٧﴾ وَأَمَّا مَنْ ءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَلَهُۥ جَزَآءً
ٱلْحُسْنَىٰ ۖ وَسَنَقُولُ لَهُۥ مِنْ أَمْرِنَا يُسْرًا ﴿٨٨﴾ ثُمَّ أَتْبَعَ سَبَبًا ﴿٨٩﴾ حَتَّىٰٓ
إِذَا بَلَغَ مَطْلِعَ ٱلشَّمْسِ وَجَدَهَا تَطْلُعُ عَلَىٰ قَوْمٍ لَّمْ نَجْعَل لَّهُم مِّن
دُونِهَا سِتْرًا ﴿٩٠﴾ كَذَٰلِكَ ۖ وَقَدْ أَحَطْنَا بِمَا لَدَيْهِ خُبْرًا ﴿٩١﴾ ثُمَّ
أَتْبَعَ سَبَبًا ﴿٩٢﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ بَيْنَ ٱلسَّدَّيْنِ وَجَدَ مِن دُونِهِمَا قَوْمًا
لَّا يَكَادُونَ يَفْقَهُونَ قَوْلًا ﴿٩٣﴾ قَالُوا۟ يَٰذَا ٱلْقَرْنَيْنِ إِنَّ يَأْجُوجَ
وَمَأْجُوجَ مُفْسِدُونَ فِى ٱلْأَرْضِ فَهَلْ نَجْعَلُ لَكَ خَرْجًا عَلَىٰٓ أَن
تَجْعَلَ بَيْنَنَا وَبَيْنَهُمْ سَدًّا ﴿٩٤﴾ قَالَ مَا مَكَّنِّى فِيهِ رَبِّى خَيْرٌ فَأَعِينُونِى
بِقُوَّةٍ أَجْعَلْ بَيْنَكُمْ وَبَيْنَهُمْ رَدْمًا ﴿٩٥﴾ ءَاتُونِى زُبَرَ ٱلْحَدِيدِ ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا سَاوَىٰ
بَيْنَ ٱلصَّدَفَيْنِ قَالَ ٱنفُخُوا۟ ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَعَلَهُۥ نَارًا قَالَ ءَاتُونِىٓ أُفْرِغْ عَلَيْهِ
قِطْرًا ﴿٩٦﴾ فَمَا ٱسْطَٰعُوٓا۟ أَن يَظْهَرُوهُ وَمَا ٱسْتَطَٰعُوا۟ لَهُۥ نَقْبًا ﴿٩٧﴾

(84) Lalle Mu Muka kafa shi a bayan ƙasa, Muka kuma ba shi hanyar cimma duk wani muradinsa

(85) Sai ya bi hanya

(86) Har sai da ya isa mafaɗar rana, sai ya same ta tana faɗuwa ne cikin wani marmaro haɗe da baƙin taɓo mai wari, ya kuma sami wasu mutane a wurinta, Muka ce: "Ya Zulƙarnaini, ko dai ka azabtar (da su), ko kuma ka kyautata musu."

(87) (Zulƙarnaini) ya ce: "Amma wanda ya yi zalunci to za mu azabtar da shi, sannan a mayar da shi zuwa ga Ubangijinsa (shi ma) Ya yi masa mummunar azab

a

(88) "Amma kuma wanda ya yi imani ya kuma yi aiki nagari, to yana da mafi kyan sakamako, kuma za mu faɗa masa tattausar (magana) game da al'amarinmu."

(89) Sannan ya kama hanya

(90) Har dai lokacin da ya isa mahudar rana, ya same ta tana ɓullowa ne a kan wasu mutane da ba Mu sanya musu wata kariya ba daga gare ta[1]

(91) Kamar haka (ya yi hukunci watau irin yadda ya yi a mafaɗar rana), haƙiƙa kuma Mun kewaye da sanin (duk) abin da ke tare da shi (Zulƙarnaini)

(92) Sannan ya kama hanya

(93) Har ya iso (wani gari) tsakanin duwatsu biyu, ya kuma sami wasu mutane a gabansu (watau duwatsun) waɗanda ba sa fahimtar wata magana

(94) Suka ce: "Ya Zulƙarnaini, lalle Yajuju da Majuju (mutane ne) masu ɓarna a bayan ƙasa, to ko za mu iya biyan ka wata jinga don ka sanya wani shamaki tsakaninmu da su?"

(95) Ya ce, "Abin da Ubangijina Ya ba ni ya fi (abin da za ku ba ni), sai dai ku taimake ni da ƙarfi (don) in sanya shamaki tsakaninku da su

(96) "Ku kawo mini guntattakin ƙarafa"; har dai lokacin da ya daidaita (ginin da) duwatsun nan biyu, sai ya ce: "Ku hura wuta da zugazuginku"; har dai yayin da ya mai da shi wuta, sai ya ce: "Ku kawo min narkakkiyar dalma in zuba a kansu."

(97) Saboda haka ba su samu ikon su haura shi ba, ba su kuma sami ikon huda shi ba

(1) Watau ba su da gidaje, kuma a inda suke babu bishiyoyi babu duwatsu da za su fake a inuwoyinsu, kuma ƙasar ba ta ɗaukan gine-gine.

قَالَ هَٰذَا رَحْمَةٌ مِّن رَّبِّي ۖ فَإِذَا جَاءَ وَعْدُ رَبِّي جَعَلَهُ دَكَّاءَ ۖ وَكَانَ وَعْدُ رَبِّي
حَقًّا ﴿٩٨﴾ وَتَرَكْنَا بَعْضَهُمْ يَوْمَئِذٍ يَمُوجُ فِي بَعْضٍ ۖ وَنُفِخَ فِي الصُّورِ
فَجَمَعْنَاهُمْ جَمْعًا ﴿٩٩﴾ وَعَرَضْنَا جَهَنَّمَ يَوْمَئِذٍ لِّلْكَافِرِينَ عَرْضًا ﴿١٠٠﴾
الَّذِينَ كَانَتْ أَعْيُنُهُمْ فِي غِطَاءٍ عَن ذِكْرِي وَكَانُوا لَا يَسْتَطِيعُونَ سَمْعًا
﴿١٠١﴾ أَفَحَسِبَ الَّذِينَ كَفَرُوا أَن يَتَّخِذُوا عِبَادِي مِن دُونِي أَوْلِيَاءَ ۚ إِنَّا
أَعْتَدْنَا جَهَنَّمَ لِلْكَافِرِينَ نُزُلًا ﴿١٠٢﴾ قُلْ هَلْ نُنَبِّئُكُمْ بِالْأَخْسَرِينَ أَعْمَالًا
﴿١٠٣﴾ الَّذِينَ ضَلَّ سَعْيُهُمْ فِي الْحَيَاةِ الدُّنْيَا وَهُمْ يَحْسَبُونَ أَنَّهُمْ يُحْسِنُونَ
صُنْعًا ﴿١٠٤﴾ أُولَٰئِكَ الَّذِينَ كَفَرُوا بِآيَاتِ رَبِّهِمْ وَلِقَائِهِ فَحَبِطَتْ
أَعْمَالُهُمْ فَلَا نُقِيمُ لَهُمْ يَوْمَ الْقِيَامَةِ وَزْنًا ﴿١٠٥﴾ ذَٰلِكَ جَزَاؤُهُمْ جَهَنَّمُ
بِمَا كَفَرُوا وَاتَّخَذُوا آيَاتِي وَرُسُلِي هُزُوًا ﴿١٠٦﴾ إِنَّ الَّذِينَ آمَنُوا وَعَمِلُوا
الصَّالِحَاتِ كَانَتْ لَهُمْ جَنَّاتُ الْفِرْدَوْسِ نُزُلًا ﴿١٠٧﴾ خَالِدِينَ فِيهَا
لَا يَبْغُونَ عَنْهَا حِوَلًا ﴿١٠٨﴾ قُل لَّوْ كَانَ الْبَحْرُ مِدَادًا لِّكَلِمَاتِ رَبِّي لَنَفِدَ
الْبَحْرُ قَبْلَ أَن تَنفَدَ كَلِمَاتُ رَبِّي وَلَوْ جِئْنَا بِمِثْلِهِ مَدَدًا ﴿١٠٩﴾ قُلْ إِنَّمَا
أَنَا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ يُوحَىٰ إِلَيَّ أَنَّمَا إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَاحِدٌ ۖ فَمَن كَانَ يَرْجُو
لِقَاءَ رَبِّهِ فَلْيَعْمَلْ عَمَلًا صَالِحًا وَلَا يُشْرِكْ بِعِبَادَةِ رَبِّهِ أَحَدًا ﴿١١٠﴾

(98) Ya ce, “Wannan rahama ce daga Ubangijina; sai dai idan alƙawarin Ubangijina ya zo, (watau tashin alƙiyama) to zai mai da shi daga-daga; alƙawarin Ubangijina kuwa ya tabbata gaskiya ne.”
(99) Kuma Muka bar sashinsu (mutane) a wannan rana yana cakuɗa da wani sashi[1]; aka kuma busa ƙaho, sannan Muka tattara su gaba ɗaya
(100) Muka kuma bijiro da (wutar) Jahannama a wannan ranar ga kafirai (su gan ta) ƙuru-ƙuru(101) (Su ne) waɗanda idanuwansu suka makance daga ambatona, suka kuma kasance ba sa iya jin (gaskiya)(102) Yanzu waɗanda suka kafirta suna tsammanin su riƙi wasu bayina ababen bauta ba Ni ba? Lalle Mun tanadi Jahannama ta zama masauki ga kafirai
(103)Ka ce (da su): “Ba na ba ku labarin waɗanda suka fi asarar ayyukansu ba? (104) “(Su ne) waɗanda aikinsu ya ɓace a rayuwarsu ta duniya alhali kuwa su suna tsammanin suna kyautata aiki ne.” (105) Waɗannan (su ne) waɗanda suka kafirce wa ayoyin Ubangijinsu da kuma gamuwa da shi, sai ayyukansu suka lalace, ba za Mu sanya musu wani ma’auni ba a ranar alƙiyama (106) Wannan shi ne sakamakonsu, Jahannama, saboda kafircewa da suka yi suka kuma riƙi ayoyina da manzannina abin yi wa izgili(107) Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari to Aljannar Firdausi[2] ita ce ta kasance masaukinsu. (108) Suna masu dawwama a cikinta, ba sa neman wani musaya da ita(109) Ka ce (da su): “Da kogi zai zamanto tawada don (rubuta) kalmomin Ubangijina[3], to lalle da kogin ya ƙare kafin kalmomin Ubangijina su ƙare, ko da kuwa Mun zo da ƙarin wasu (koguna) kamarsa (110) Ka ce: “Ni dai mutum ne kawai kamarku da ake yi mini wahayi cewa abin bautarku abin bauta ne Ɗaya; don haka wanda ya kasance yana tsoron gamuwa da Ubangijinsa, to sai ya yi aiki nagari, kada kuma ya tara wani cikin bautar Ubangijinsa.”

(1) Wannan zai iya ɗaukar ma’anar cewa, ranar da Yajuju da Majuju za su fito da yawa suna gauraya da mutane suna masu ɓarna. A wata ma’anar kuma ana nufin ranar alƙiyama da mutane da aljannu za su gauraya da juna wuri ɗaya.

(2) Aljannar Firdausi ita ce ƙololuwar Aljanna mafi daraja.

(3) Kalmomin Allah su ne yalwar siffofinsa da iliminsa da ƙudurarsa.

سُورَةُ مَرۡيَمَ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

كٓهيعٓصٓ ﴿١﴾ ذِكۡرُ رَحۡمَتِ رَبِّكَ عَبۡدَهُۥ زَكَرِيَّآ ﴿٢﴾ إِذۡ
نَادَىٰ رَبَّهُۥ نِدَآءً خَفِيًّا ﴿٣﴾ قَالَ رَبِّ إِنِّي وَهَنَ ٱلۡعَظۡمُ مِنِّي
وَٱشۡتَعَلَ ٱلرَّأۡسُ شَيۡبٗا وَلَمۡ أَكُنۢ بِدُعَآئِكَ رَبِّ شَقِيّٗا
﴿٤﴾ وَإِنِّي خِفۡتُ ٱلۡمَوَٰلِيَ مِن وَرَآءِي وَكَانَتِ ٱمۡرَأَتِي
عَاقِرٗا فَهَبۡ لِي مِن لَّدُنكَ وَلِيّٗا ﴿٥﴾ يَرِثُنِي وَيَرِثُ مِنۡ
ءَالِ يَعۡقُوبَۖ وَٱجۡعَلۡهُ رَبِّ رَضِيّٗا ﴿٦﴾ يَٰزَكَرِيَّآ إِنَّا
نُبَشِّرُكَ بِغُلَٰمٍ ٱسۡمُهُۥ يَحۡيَىٰ لَمۡ نَجۡعَل لَّهُۥ مِن قَبۡلُ سَمِيّٗا
﴿٧﴾ قَالَ رَبِّ أَنَّىٰ يَكُونُ لِي غُلَٰمٞ وَكَانَتِ ٱمۡرَأَتِي عَاقِرٗا
وَقَدۡ بَلَغۡتُ مِنَ ٱلۡكِبَرِ عِتِيّٗا ﴿٨﴾ قَالَ كَذَٰلِكَ قَالَ
رَبُّكَ هُوَ عَلَيَّ هَيِّنٞ وَقَدۡ خَلَقۡتُكَ مِن قَبۡلُ وَلَمۡ تَكُ
شَيۡـٔٗا ﴿٩﴾ قَالَ رَبِّ ٱجۡعَل لِّيٓ ءَايَةٗۚ قَالَ ءَايَتُكَ أَلَّا
تُكَلِّمَ ٱلنَّاسَ ثَلَٰثَ لَيَالٖ سَوِيّٗا ﴿١٠﴾ فَخَرَجَ عَلَىٰ قَوۡمِهِۦ مِنَ
ٱلۡمِحۡرَابِ فَأَوۡحَىٰٓ إِلَيۡهِمۡ أَن سَبِّحُواْ بُكۡرَةٗ وَعَشِيّٗا ﴿١١﴾

Sura Maryam

(1) KAF HA YA AIN SAD[1]
(2) (Wannan) ambaton rahamar Ubangijinka ne (da Ya yi wa) Bawansa Zakariyya
(3) Lokacin da ya kira Ubangijinsa (ya roƙe Shi) cikin asiri
(4) Ya ce: "Ya Ubangiji lalle ƙasusuwana sun yi rauni, kaina kuma ya yi fari fat da furfura, Ubangijina ban kuma zama mai taɓewa ba game da roƙon Ka
(5) "Kuma lalle ni na ji tsoron dangina a bayana[2], matata kuma ga ta bakarara ce, saboda haka Ka yi mini baiwa daga gare Ka ta (ɗa) majiɓinci
(6) "(Wanda) zai gaje ni[3] ya kuma gaji iyalan Ya'aƙub; Ubangijina kuma Ka sanya shi yardajje (a wurinka)."
(7)(Aka ce): Ya Zakariyya, lalle Muna yi maka albishir da samun ɗa, sunansa Yahya, ba Mu kuwa sanya wa wani sunan ba gabaninsa
(8) Ya ce: "Ubangijina ta ƙaƙa zan samu ɗa, alhali kuwa matata ta zamanto bakarara ce, ni kuma ga shi na tsufa tukuf"
(9) Ya ce: "Kamar haka Ubangijinka Ya faɗa (cewa): 'Shi (wannan) mai sauƙi ne a wurina, don kuwa haƙiƙa Na halicce ka alhalin ba ka zama komai ba.'"
(10) Ya ce: "Ubangijina Ka sanya mini wata alama." Sai (Allah) Ya ce: "Alamarka ita ce ka kasa yi wa mutane magana (tsawon) kwana uku daidai."
(11) Sannan (Zakariyya) ya fito wa mutanensa daga wurin ibada ya yi musu ishara cewa: "Ku yi tasbihi safe da maraice."

(1) Duba Suratul Baƙara, aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Watau kada su watsar da kulawa da addini, su shagala da neman abincinsu.

(3) Watau ya gaji ilimi da annabta da shugabantar gudanar da harkokin addini.

يَٰيَحۡيَىٰ خُذِ ٱلۡكِتَٰبَ بِقُوَّةٖۖ وَءَاتَيۡنَٰهُ ٱلۡحُكۡمَ صَبِيّٗا ١٢
وَحَنَانٗا مِّن لَّدُنَّا وَزَكَوٰةٗۖ وَكَانَ تَقِيّٗا ١٣ وَبَرَّۢا بِوَٰلِدَيۡهِ وَلَمۡ
يَكُن جَبَّارًا عَصِيّٗا ١٤ وَسَلَٰمٌ عَلَيۡهِ يَوۡمَ وُلِدَ وَيَوۡمَ يَمُوتُ
وَيَوۡمَ يُبۡعَثُ حَيّٗا ١٥ وَٱذۡكُرۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ مَرۡيَمَ إِذِ ٱنتَبَذَتۡ
مِنۡ أَهۡلِهَا مَكَانٗا شَرۡقِيّٗا ١٦ فَٱتَّخَذَتۡ مِن دُونِهِمۡ حِجَابٗا
فَأَرۡسَلۡنَآ إِلَيۡهَا رُوحَنَا فَتَمَثَّلَ لَهَا بَشَرٗا سَوِيّٗا ١٧ قَالَتۡ إِنِّيٓ
أَعُوذُ بِٱلرَّحۡمَٰنِ مِنكَ إِن كُنتَ تَقِيّٗا ١٨ قَالَ إِنَّمَآ أَنَا۠ رَسُولُ
رَبِّكِ لِأَهَبَ لَكِ غُلَٰمٗا زَكِيّٗا ١٩ قَالَتۡ أَنَّىٰ يَكُونُ لِي
غُلَٰمٞ وَلَمۡ يَمۡسَسۡنِي بَشَرٞ وَلَمۡ أَكُ بَغِيّٗا ٢٠ قَالَ كَذَٰلِكِ
قَالَ رَبُّكِ هُوَ عَلَيَّ هَيِّنٞۖ وَلِنَجۡعَلَهُۥٓ ءَايَةٗ لِّلنَّاسِ وَرَحۡمَةٗ
مِّنَّاۚ وَكَانَ أَمۡرٗا مَّقۡضِيّٗا ٢١ ۞ فَحَمَلَتۡهُ فَٱنتَبَذَتۡ بِهِۦ
مَكَانٗا قَصِيّٗا ٢٢ فَأَجَآءَهَا ٱلۡمَخَاضُ إِلَىٰ جِذۡعِ ٱلنَّخۡلَةِ
قَالَتۡ يَٰلَيۡتَنِي مِتُّ قَبۡلَ هَٰذَا وَكُنتُ نَسۡيٗا مَّنسِيّٗا ٢٣
فَنَادَىٰهَا مِن تَحۡتِهَآ أَلَّا تَحۡزَنِي قَدۡ جَعَلَ رَبُّكِ تَحۡتَكِ سَرِيّٗا ٢٤
وَهُزِّيٓ إِلَيۡكِ بِجِذۡعِ ٱلنَّخۡلَةِ تُسَٰقِطۡ عَلَيۡكِ رُطَبٗا جَنِيّٗا ٢٥

(12) (Allah ya ce): “Ya Yahaya, ka riƙi littafin (Attaura) da ƙarfi”; Muka kuma ba shi annabci tun yana ƙarami
(13) Kuma (Muka hore masa) tausayi daga gare Mu da tsarkin (zuciya), ya kuma kasance mai kiyaye dokokin Allah ne
(14) Kuma mai biyayya ga mahaifansa, bai kuma zamanto mai taurin kai mai saɓa wa (umarnin Allah) ba
(15) Kuma aminci ya tabbata a gare shi ranar da aka haife shi da kuma ranar da zai mutu da kuma ranar da za a tashe shi rayayye
(16) Kuma ka ambaci (labarin) Maryamu a cikin (wannan) Littafi lokacin da ta ƙaurace wa mutanenta zuwa wani wuri a nahiyar gabas
(17) Sai ta saka shamaki tsakaninta da su (mutanen nata), to sai Muka aiko mata da Ruhinmu (shi ne Jibrilu) ya bayyana gare ta da surar daidaitaccen mutum
(18) Ta ce: “Lalle ina neman Allah ya tsare ni daga gare ka idan ka zamanto mai taƙawa ne.”
(19) Ya ce: “Ni manzo ne kawai na Ubangijinki na zo don in yi miki baiwar ɗa tsarkakakke.”
(20) Ta ce: “Ta ƙaƙa zan samu ɗa, alhalin kuwa wani namiji bai taɓa shafa ta ba, kuma ni ban zamanto mazinaciya ba?”
(21) (Mala’ika) ya ce: “Kamar haka ne Ubangijinki Ya faɗa (cewa): “Shi (wannan) mai sauƙi ne a wurina, kuma don Mu mayar da shi aya ga mutane da kuma rahama daga gare Mu, kuma (yin haka) ya zamanto al’amari ne tabbatacce (rubuce a Lauhul-Mahafuzu).”
(22) Sai ta ɗauki cikinsa sannan ta (tafi) da shi wani wuri mai nisa
(23) Sai ciwon naƙuda ya tilasta mata zuwa ga kututturen dabino, ta ce: “Ina ma na mutu tun kafin wannan (abu ya faru), na kuma kasance yasasshiya, mantacciya!”
(24) Sai ya kira ta daga ƙarƙashinta[1] cewa: “Kada ki yi baƙin ciki, haƙiƙa Ubangijinki Ya sanya ƙorama a ƙarƙashinki
(25) “Ki kuma girgiza kututturen dabinon nan zai zubo miki da lubiyar dabino nunanniya

(1) Watau Annabi Isa ( ).

فَكُلِي وَٱشْرَبِي وَقَرِّي عَيْنًا ۖ فَإِمَّا تَرَيِنَّ مِنَ ٱلْبَشَرِ أَحَدًا فَقُولِيٓ
إِنِّي نَذَرْتُ لِلرَّحْمَٰنِ صَوْمًا فَلَنْ أُكَلِّمَ ٱلْيَوْمَ إِنسِيًّا ﴿٢٦﴾ فَأَتَتْ
بِهِۦ قَوْمَهَا تَحْمِلُهُۥ ۖ قَالُوا۟ يَٰمَرْيَمُ لَقَدْ جِئْتِ شَيْـًٔا فَرِيًّا ﴿٢٧﴾
يَٰٓأُخْتَ هَٰرُونَ مَا كَانَ أَبُوكِ ٱمْرَأَ سَوْءٍ وَمَا كَانَتْ
أُمُّكِ بَغِيًّا ﴿٢٨﴾ فَأَشَارَتْ إِلَيْهِ ۖ قَالُوا۟ كَيْفَ نُكَلِّمُ مَن كَانَ فِى
ٱلْمَهْدِ صَبِيًّا ﴿٢٩﴾ قَالَ إِنِّى عَبْدُ ٱللَّهِ ءَاتَىٰنِىَ ٱلْكِتَٰبَ وَجَعَلَنِى
نَبِيًّا ﴿٣٠﴾ وَجَعَلَنِى مُبَارَكًا أَيْنَ مَا كُنتُ وَأَوْصَىٰنِى بِٱلصَّلَوٰةِ
وَٱلزَّكَوٰةِ مَا دُمْتُ حَيًّا ﴿٣١﴾ وَبَرًّۢا بِوَٰلِدَتِى وَلَمْ يَجْعَلْنِى
جَبَّارًا شَقِيًّا ﴿٣٢﴾ وَٱلسَّلَٰمُ عَلَىَّ يَوْمَ وُلِدتُّ وَيَوْمَ أَمُوتُ
وَيَوْمَ أُبْعَثُ حَيًّا ﴿٣٣﴾ ذَٰلِكَ عِيسَى ٱبْنُ مَرْيَمَ ۚ قَوْلَ ٱلْحَقِّ
ٱلَّذِى فِيهِ يَمْتَرُونَ ﴿٣٤﴾ مَا كَانَ لِلَّهِ أَن يَتَّخِذَ مِن وَلَدٍ ۖ سُبْحَٰنَهُۥٓ
إِذَا قَضَىٰٓ أَمْرًا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿٣٥﴾ وَإِنَّ ٱللَّهَ رَبِّى وَرَبُّكُمْ
فَٱعْبُدُوهُ ۚ هَٰذَا صِرَٰطٌ مُّسْتَقِيمٌ ﴿٣٦﴾ فَٱخْتَلَفَ ٱلْأَحْزَابُ مِنۢ
بَيْنِهِمْ ۖ فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِن مَّشْهَدِ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿٣٧﴾ أَسْمِعْ بِهِمْ
وَأَبْصِرْ يَوْمَ يَأْتُونَنَا لَٰكِنِ ٱلظَّٰلِمُونَ ٱلْيَوْمَ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٣٨﴾

(26) “Don haka ki ci, ki sha, kuma ki kwantar da hankalinki; kuma duk mutumin da kika gani (ya yi magana da ke), sai ki yi nuni da cewa: “Na ɗauki alƙawari ga Allah na kame bakina, ba zan yi magana da wani mutum ba yau.”

(27) Sai ta zo wa mutanenta da shi tana ɗauke da shi; suka ce: “Ya Maryamu, haƙiƙa kin zo da babban abu!

(28) “Ya ke ‘yar’uwar Haruna[1], mahaifinki bai kasance lalataccen mutum ba, mahaifiyarki ma ba mazinaciya ba.”

(29) Sai ta nuna shi; (sai) suka ce: “Ta ƙaƙa za mu yi magana da wanda yake ɗan jariri cikin shimfiɗar jego?”?”.

(30) (Isa) ya ce (da su): “Lalle ni bawan Allah ne, Ya ba ni littafi Ya kuma sanya ni Annabi

(31) “Ya kuma sanya ni mai albarka a duk inda nake, kuma Ya umarce ni da yin salla da kuma ba da zakka matuƙar ina raye

(32) “Kuma mai biyayya ga mahaifiyata, bai kuma sanya ni mai girman kai mai saɓo ba

(33) “Amincin (Allah) kuma ya tabbata a gare ni ranar da aka haife ni da ranar da zan mutu da kuma ranar da za a tashe ni rayayye.”

(34) Wannan shi ne Isa ɗan Maryamu. Zance na gaskiya wanda a kansa ne suke ta shakka suna jayayya (da junansu)

(35) Ba zai yiwu a ce Allah yana da ɗa ba; tsarki ya tabbata a gare Shi. Idan Ya nufi zartar da wani lamari sai kawai Ya ce masa: “Kasance”, sai ko ya kasance

(36) “Lalle kuma Allah shi ne Ubangijina kuma Ubangijinku, sai ku bauta masa. Wannan ita ce hanya madaidaiciya.”

(37) Sai ƙungiyoyin suka sassaɓa a tsakaninsu; to bone ya tabbata ga waɗanda suka kafirta daga halartar rana mai girma (ita ce alƙiyama)

(38) Ka yi mamakin jinsu da ganinsu a ranar da za su zo mana; sai dai azzalumai a wannan rana suna cikin ɓata mabayyani

(1) Wani mutum ne mai ibada da kamun kai, ana ce masa Haruna. Wasu malaman sun ce ɗan’uwanta ne.

وَأَنذِرْهُمْ يَوْمَ ٱلْحَسْرَةِ إِذْ قُضِىَ ٱلْأَمْرُ وَهُمْ فِى غَفْلَةٍ وَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿٣٩﴾ إِنَّا نَحْنُ نَرِثُ ٱلْأَرْضَ وَمَنْ عَلَيْهَا وَإِلَيْنَا يُرْجَعُونَ ﴿٤٠﴾ وَٱذْكُرْ فِى ٱلْكِتَٰبِ إِبْرَٰهِيمَ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ صِدِّيقًا نَّبِيًّا ﴿٤١﴾ إِذْ قَالَ لِأَبِيهِ يَٰٓأَبَتِ لِمَ تَعْبُدُ مَا لَا يَسْمَعُ وَلَا يُبْصِرُ وَلَا يُغْنِى عَنكَ شَيْـًٔا ﴿٤٢﴾ يَٰٓأَبَتِ إِنِّى قَدْ جَآءَنِى مِنَ ٱلْعِلْمِ مَا لَمْ يَأْتِكَ فَٱتَّبِعْنِىٓ أَهْدِكَ صِرَٰطًا سَوِيًّا ﴿٤٣﴾ يَٰٓأَبَتِ لَا تَعْبُدِ ٱلشَّيْطَٰنَ ۖ إِنَّ ٱلشَّيْطَٰنَ كَانَ لِلرَّحْمَٰنِ عَصِيًّا ﴿٤٤﴾ يَٰٓأَبَتِ إِنِّىٓ أَخَافُ أَن يَمَسَّكَ عَذَابٌ مِّنَ ٱلرَّحْمَٰنِ فَتَكُونَ لِلشَّيْطَٰنِ وَلِيًّا ﴿٤٥﴾ قَالَ أَرَاغِبٌ أَنتَ عَنْ ءَالِهَتِى يَٰٓإِبْرَٰهِيمُ ۖ لَئِن لَّمْ تَنتَهِ لَأَرْجُمَنَّكَ ۖ وَٱهْجُرْنِى مَلِيًّا ﴿٤٦﴾ قَالَ سَلَٰمٌ عَلَيْكَ ۖ سَأَسْتَغْفِرُ لَكَ رَبِّىٓ ۖ إِنَّهُۥ كَانَ بِى حَفِيًّا ﴿٤٧﴾ وَأَعْتَزِلُكُمْ وَمَا تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَأَدْعُوا۟ رَبِّى عَسَىٰٓ أَلَّآ أَكُونَ بِدُعَآءِ رَبِّى شَقِيًّا ﴿٤٨﴾ فَلَمَّا ٱعْتَزَلَهُمْ وَمَا يَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَهَبْنَا لَهُۥٓ إِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ ۖ وَكُلًّا جَعَلْنَا نَبِيًّا ﴿٤٩﴾ وَوَهَبْنَا لَهُم مِّن رَّحْمَتِنَا وَجَعَلْنَا لَهُمْ لِسَانَ صِدْقٍ عَلِيًّا ﴿٥٠﴾ وَٱذْكُرْ فِى ٱلْكِتَٰبِ مُوسَىٰٓ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ مُخْلَصًا وَكَانَ رَسُولًا نَّبِيًّا ﴿٥١﴾

(39) Ka kuma gargaɗe su game da ranar nadama, lokacin da aka ƙare hisabi, alhali kuwa su (a duniya) suna cikin rafkana kuma su ba sa yin imani

(40) Lalle Mu ne za Mu gaje ƙasa da wanda yake bayanta kuma gare Mu ne za a komar da su

(41) Kuma ka ambaci (labarin) Ibrahimu a cikin (wannan) littafi (Alƙur'ani). Lalle shi mutum ne mai yawan gaskiya (kuma) Annabi

(42) Lokacin da ya ce da Babansa: "Ya Babana, me ya sa kake bauta wa abin da ba ya ji ba kuma ya gani, kuma ba ya yi maka maganin komai?

(43) "Ya Babana, Lalle ni haƙiƙa wani ilimi ya zo mini wanda kai bai zo maka ba, to ka bi ni zan shiryar da kai hanya madaidaiciya

(44) "Ya Babana, kada ka bauta wa Shaiɗan ; lalle Shaiɗan ya kasance mai saɓo ne ga (Allah) Mai rahama

(45) "Ya Babana, lalle ni fa ina tsoron azaba ta shafe ka daga (Allah) Mai rahama, sai ka zama majiɓincin Shaiɗan."

(46) (Babansa) ya ce: "Yanzu Ibrahimu ƙyamar iyayen gijina kake yi? To tabbas idan ba ka bari ba lalle zan jefe ka; ka ɓace min da gani na tsawon lokaci!"

(47) (Annabi Ibrahimu) ya ce: "Aminci ya tabbata gare ka; zan nema maka gafarar Ubangijina[1]; don ko lalle Shi ya tabbata Mai haba-haba ne da ni

(48) "Zan kuwa ƙaurace muku ku da abin da kuke bauta wa wanda ba Allah ba, in kuma roƙi Ubangijina, na kuma sa tsammanin cewa ba zan zama taɓaɓɓe ba game da roƙon Ubangijina."

(49) To lokacin da ya ƙaurace musu tare da abin da suke bauta wa wanda ba Allah ba, sai Muka yi masa baiwa da Is'haƙa da Ya'aƙubu; kowannensu kuma Muka ba shi annabta

(50) Muka kuma yi musu baiwa da rahamarmu, kuma Muka sanya musu kyakkyawan ambato maɗaukaki[2]

(51) Ka kuma ambaci (labarin) Musa cikin (wannan) Littafi (Alƙur'ani). Lalle shi zaɓaɓɓe ne, ya kuma kasance Annabi ne Manzo

(1) Ya faɗi haka ne kafin Allah ya hana shi nema masa gafara

(2) Watau ya sa suka zamanto ababen yabo mai ɗorewa a gun kowa.

وَنَدَيْنَٰهُ مِن جَانِبِ ٱلطُّورِ ٱلْأَيْمَنِ وَقَرَّبْنَٰهُ نَجِيًّا ﴿٥٢﴾ وَوَهَبْنَا لَهُۥ مِن
رَّحْمَتِنَآ أَخَاهُ هَٰرُونَ نَبِيًّا ﴿٥٣﴾ وَٱذْكُرْ فِى ٱلْكِتَٰبِ إِسْمَٰعِيلَ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ
صَادِقَ ٱلْوَعْدِ وَكَانَ رَسُولًا نَّبِيًّا ﴿٥٤﴾ وَكَانَ يَأْمُرُ أَهْلَهُۥ بِٱلصَّلَوٰةِ
وَٱلزَّكَوٰةِ وَكَانَ عِندَ رَبِّهِۦ مَرْضِيًّا ﴿٥٥﴾ وَٱذْكُرْ فِى ٱلْكِتَٰبِ إِدْرِيسَ ۚ إِنَّهُۥ
كَانَ صِدِّيقًا نَّبِيًّا ﴿٥٦﴾ وَرَفَعْنَٰهُ مَكَانًا عَلِيًّا ﴿٥٧﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ أَنْعَمَ
ٱللَّهُ عَلَيْهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مِن ذُرِّيَّةِ ءَادَمَ وَمِمَّنْ حَمَلْنَا مَعَ نُوحٍ وَمِن
ذُرِّيَّةِ إِبْرَٰهِيمَ وَإِسْرَٰٓءِيلَ وَمِمَّنْ هَدَيْنَا وَٱجْتَبَيْنَا ۚ إِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ
ءَايَٰتُ ٱلرَّحْمَٰنِ خَرُّوا۟ سُجَّدًا وَبُكِيًّا ﴿٥٨﴾ ۩ فَخَلَفَ مِنۢ بَعْدِهِمْ
خَلْفٌ أَضَاعُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَٱتَّبَعُوا۟ ٱلشَّهَوَٰتِ ۖ فَسَوْفَ يَلْقَوْنَ غَيًّا
﴿٥٩﴾ إِلَّا مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَأُو۟لَٰٓئِكَ يَدْخُلُونَ ٱلْجَنَّةَ
وَلَا يُظْلَمُونَ شَيْـًٔا ﴿٦٠﴾ جَنَّٰتِ عَدْنٍ ٱلَّتِى وَعَدَ ٱلرَّحْمَٰنُ عِبَادَهُۥ
بِٱلْغَيْبِ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ وَعْدُهُۥ مَأْتِيًّا ﴿٦١﴾ لَّا يَسْمَعُونَ فِيهَا لَغْوًا إِلَّا
سَلَٰمًا ۖ وَلَهُمْ رِزْقُهُمْ فِيهَا بُكْرَةً وَعَشِيًّا ﴿٦٢﴾ تِلْكَ ٱلْجَنَّةُ ٱلَّتِى
نُورِثُ مِنْ عِبَادِنَا مَن كَانَ تَقِيًّا ﴿٦٣﴾ وَمَا نَتَنَزَّلُ إِلَّا بِأَمْرِ رَبِّكَ ۖ لَهُۥ
مَا بَيْنَ أَيْدِينَا وَمَا خَلْفَنَا وَمَا بَيْنَ ذَٰلِكَ ۚ وَمَا كَانَ رَبُّكَ نَسِيًّا ﴿٦٤﴾

(52) Muka kuma kira shi a gefen dutsen Duri na dama, Muka kuma kusanto shi yana mai ganawa (da Mu)

(53) Kuma cikin rahamarmu Muka yi masa baiwa da dan'uwansa Haruna (shi ma) Annabi

(54) Kuma ka ambaci (labarin) Isma'ila a cikin (wannan) Littafi (Alkur'ani). Lalle shi ya kasance mai gaskiyar alkawari ne, kuma ya kasance Annabi ne, Manzo

(55) Kuma ya zamanto yana umartar iyalinsa da (tsai da) salla da kuma (ba da) zakka, kuma shi yardajje ne a wurin Ubangijinsa

(56) Kuma ka ambaci (labarin) Idrisu a cikin (wannan) Littafi (Alkur'ani). Lalle shi ya kasance mai yawan gaskiya ne, Annabi

(57) Muka kuma daukaka shi daraja madaukakiya[1]

(58) Wadannan su ne annabawa wadanda Allah Ya yi ni'ima a gare su, daga zuriyar Adamu, da kuma wadanda Muka dauko (a jirgin ruwa) tare da Nuhu, daga kuma zuriyar Ibrahimu da Isra'ila (watau Ya'akubu), da kuma wadanda Muka shiryar da su Muka kuma zabe su. Idan ana karanta musu ayoyin (Allah) Mai rahama sai su fadi su yi sujjada suna kuka

(59) Sai wasu suka maye gurbinsu bayansu wadanda suka tozarta salla suka kuma bi sha'awace-sha'awacen (duniya na sabo); to ba da dadewa ba za su hadu da mummunan sharri (a Jahannama)

(60) Sai dai wanda ya tuba ya yi imani ya kuma yi aiki na gari, to wadannan za su shiga Aljanna, kuma ba za a tauye musu komai ba

(61) (Watau) gidajen Aljanna na dindindin wadanda (Allah) Mai rahama Ya yi wa bayinsa alkawari da su alhali ba su gan su ba. Lalle alkawarinsa kuwa ya tabbata mai zuwa ne

(62) Ba za su ji wani zancen banza ba a cikinsu sai sallama (daga mala'iku); kuma arzikinsu na nan tare da su a cikinsu safe da yamma

(63) Waccan ita ce Aljannar da za Mu gadar da ita ga wanda ya zamo mai takawa daga cikin bayinmu

(64) (Mala'ika Jibrilu ya ce): "Ba ma sauka sai da umarnin Ubangijinka[2]; abin da yake gabanmu da wanda yake bayanmu da kuma abin da yake tsakanin wadannan (duka) nasa ne. Ubangijinka kuma bai zama Mai mantuwa ba".

(1) A Mi'iraji da Annabi ( ) ya yi ya hadu da shi a sama ta hudu.

(2) Allah ( ) shi ne ya umarci Jibrilu ( ) ya ba wa Annabi ( ) amsar tambayar da ya yi masa game da rashin zuwansa na wani dan lokaci.

رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا فَٱعۡبُدۡهُ وَٱصۡطَبِرۡ لِعِبَٰدَتِهِۦۚ
هَلۡ تَعۡلَمُ لَهُۥ سَمِيّٗا ٦٥ وَيَقُولُ ٱلۡإِنسَٰنُ أَءِذَا مَا مِتُّ لَسَوۡفَ
أُخۡرَجُ حَيًّا ٦٦ أَوَلَا يَذۡكُرُ ٱلۡإِنسَٰنُ أَنَّا خَلَقۡنَٰهُ مِن قَبۡلُ
وَلَمۡ يَكُ شَيۡـٔٗا ٦٧ فَوَرَبِّكَ لَنَحۡشُرَنَّهُمۡ وَٱلشَّيَٰطِينَ ثُمَّ
لَنُحۡضِرَنَّهُمۡ حَوۡلَ جَهَنَّمَ جِثِيّٗا ٦٨ ثُمَّ لَنَنزِعَنَّ مِن كُلِّ
شِيعَةٍ أَيُّهُمۡ أَشَدُّ عَلَى ٱلرَّحۡمَٰنِ عِتِيّٗا ٦٩ ثُمَّ لَنَحۡنُ أَعۡلَمُ بِٱلَّذِينَ
هُمۡ أَوۡلَىٰ بِهَا صِلِيّٗا ٧٠ وَإِن مِّنكُمۡ إِلَّا وَارِدُهَاۚ كَانَ عَلَىٰ رَبِّكَ
حَتۡمٗا مَّقۡضِيّٗا ٧١ ثُمَّ نُنَجِّي ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ وَّنَذَرُ ٱلظَّٰلِمِينَ
فِيهَا جِثِيّٗا ٧٢ وَإِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٖ قَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَيُّ ٱلۡفَرِيقَيۡنِ خَيۡرٞ مَّقَامٗا وَأَحۡسَنُ نَدِيّٗا ٧٣
وَكَمۡ أَهۡلَكۡنَا قَبۡلَهُم مِّن قَرۡنٍ هُمۡ أَحۡسَنُ أَثَٰثٗا وَرِءۡيٗا ٧٤
قُلۡ مَن كَانَ فِي ٱلضَّلَٰلَةِ فَلۡيَمۡدُدۡ لَهُ ٱلرَّحۡمَٰنُ مَدًّاۚ حَتَّىٰٓ إِذَا رَأَوۡاْ
مَا يُوعَدُونَ إِمَّا ٱلۡعَذَابَ وَإِمَّا ٱلسَّاعَةَ فَسَيَعۡلَمُونَ مَنۡ هُوَ شَرّٞ
مَّكَانٗا وَأَضۡعَفُ جُندٗا ٧٥ وَيَزِيدُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ٱهۡتَدَوۡاْ هُدٗىۗ
وَٱلۡبَٰقِيَٰتُ ٱلصَّٰلِحَٰتُ خَيۡرٌ عِندَ رَبِّكَ ثَوَابٗا وَخَيۡرٞ مَّرَدّٗا ٧٦

(65) "(Shi ne) Ubangijin sammai da ƙasa da kuma abin da yake tsakaninsu, sai ka bauta masa kuma ka yi haƙuri ga bautarsa. Shin ka san wani tamkarsa?"

(66) Kuma mutum (watau kafiri) yana cewa: "Yanzu idan na mutu anya kuwa za a ta da ni da rai?"

(67) Yanzu shi kafiri ba zai tuna ba cewa Mu Muka halicce shi tun farko kafin ya zama komai?

(68) To na rantse da Ubangijinka lalle za Mu tashe su tare da shaiɗanu, sannan za Mu kawo su a gaban Jahannama suna a duddurƙushe

(69) Sannan daga kowace jama'a lalle za Mu ware waɗanda suka fi tsananin yi wa (Allah) Mai rahama tsaurin kai

(70) Sannan babu shakka Mu Muka fi sanin waɗanda suka fi cancanta da ƙonuwa da ita (watau wuta)

(71) Ba kuma ɗaya daga cikinku face sai ya bi ta kanta (watau wutar Jahannama). (Wannan) ya kasance tabbataccen abu abin hukuntawa a wurin Ubangijinka

(72)Sannan kuma za Mu tserar da waɗanda suka kiyaye dokokin Allah Mu kuma bar kafirai a duddurƙushe cikinta

(73) Kuma idan ana karanta musu ayoyinmu bayyanannu sai waɗanda suka kafirta su ce da waɗanda suka yi imani: "Wane ne daga cikin ƙungiyoyin nan biyu (watau muminai da kafirai) yake da mafificin matsayi da kuma mafi kyan majalisa?"

(74) Kuma al'umma nawa Muka hallaka a gabanninsu waɗanda suke da mafi kyan abin duniya da kyawun gani

(75) Ka ce (da su): "Wanda ya zamana yana cikin ɓata to (Allah) Mai rahama zai tsawaita ransa Ya yalwata masa; Har sai sanda suka ga abin da ake yi musu alƙawari da shi ne, ko dai azaba (a duniya) ko kuma tashin alƙiyama, to fa za su san wane ne ya fi mummunan matsayi da kuma (wanda) ya fi raunin mataimaka."

(76) Kuma Allah Yana ƙara shiryar da waɗanda suka bi hanyar shiriya. Wanzazzun ayyuka na gari kuma su suka fi lada a wurin Ubangijinka, suka kuma fi kyakkyawan ƙarshe

أَفَرَءَيْتَ ٱلَّذِى كَفَرَ بِـَٔايَٰتِنَا وَقَالَ لَأُوتَيَنَّ مَالًا وَوَلَدًا ﴿٧٧﴾ أَطَّلَعَ ٱلْغَيْبَ أَمِ ٱتَّخَذَ عِندَ ٱلرَّحْمَٰنِ عَهْدًا ﴿٧٨﴾ كَلَّا ۚ سَنَكْتُبُ مَا يَقُولُ وَنَمُدُّ لَهُۥ مِنَ ٱلْعَذَابِ مَدًّا ﴿٧٩﴾ وَنَرِثُهُۥ مَا يَقُولُ وَيَأْتِينَا فَرْدًا ﴿٨٠﴾ وَٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ ءَالِهَةً لِّيَكُونُوا۟ لَهُمْ عِزًّا ﴿٨١﴾ كَلَّا ۚ سَيَكْفُرُونَ بِعِبَادَتِهِمْ وَيَكُونُونَ عَلَيْهِمْ ضِدًّا ﴿٨٢﴾ أَلَمْ تَرَ أَنَّآ أَرْسَلْنَا ٱلشَّيَٰطِينَ عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ تَؤُزُّهُمْ أَزًّا ﴿٨٣﴾ فَلَا تَعْجَلْ عَلَيْهِمْ ۖ إِنَّمَا نَعُدُّ لَهُمْ عَدًّا ﴿٨٤﴾ يَوْمَ نَحْشُرُ ٱلْمُتَّقِينَ إِلَى ٱلرَّحْمَٰنِ وَفْدًا ﴿٨٥﴾ وَنَسُوقُ ٱلْمُجْرِمِينَ إِلَىٰ جَهَنَّمَ وِرْدًا ﴿٨٦﴾ لَّا يَمْلِكُونَ ٱلشَّفَٰعَةَ إِلَّا مَنِ ٱتَّخَذَ عِندَ ٱلرَّحْمَٰنِ عَهْدًا ﴿٨٧﴾ وَقَالُوا۟ ٱتَّخَذَ ٱلرَّحْمَٰنُ وَلَدًا ﴿٨٨﴾ لَّقَدْ جِئْتُمْ شَيْـًٔا إِدًّا ﴿٨٩﴾ تَكَادُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ يَتَفَطَّرْنَ مِنْهُ وَتَنشَقُّ ٱلْأَرْضُ وَتَخِرُّ ٱلْجِبَالُ هَدًّا ﴿٩٠﴾ أَن دَعَوْا۟ لِلرَّحْمَٰنِ وَلَدًا ﴿٩١﴾ وَمَا يَنۢبَغِى لِلرَّحْمَٰنِ أَن يَتَّخِذَ وَلَدًا ﴿٩٢﴾ إِن كُلُّ مَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ إِلَّآ ءَاتِى ٱلرَّحْمَٰنِ عَبْدًا ﴿٩٣﴾ لَّقَدْ أَحْصَىٰهُمْ وَعَدَّهُمْ عَدًّا ﴿٩٤﴾ وَكُلُّهُمْ ءَاتِيهِ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فَرْدًا ﴿٩٥﴾

(77) Shin kuwa ka ga wanda ya kafirce wa ayoyinmu, ya kuma ce: “Lalle tabbas za a ba ni dukiya da ‘ya’yaye?” (78) Shin ko ya san gaibu ne, ko kuwa ya sami alkawari ne a wurin (Allah) Mai rahama? (79) A’a, ba haka ba ne. Za Mu rubuta abin da yake faɗa, za Mu kuma ƙara masa azaba ninkin-ba-ninkin (80) Kuma Mu gaje abin da yake faɗa ɗin (na dukiyarsa da ‘ya’yansa), ya kuma zo mana shi kaɗai[1] (81) (Kafirai) kuma suka riƙi wasu abubuwan bauta ba Allah ba don su zama mataimaka a gare su (82) A’a, ba haka ba ne. Ba da daɗewa ba za su kafirce wa bautar da suke yi musu, su kuma zama abokan gaba a gare su (83) Shin ba ka san Mu Muka ɗora shaiɗanu a kan kafirai ba suna ingiza su (cikin ɓata) ingizawa? (84) To kada ka yi gaggawa a kansu; kawai dai Muna ƙididdige musu (kwanakinsu) ɗai da ɗai

(85) Ranar da za Mu tayar da masu taƙawa zuwa ga (Allah) Mai rahama a matsayin manyan baƙi (86) Mu kuma kora kafirai zuwa Jahannama cikin tsananin ƙishirwa (87) Ba wani mai ikon yin ceto sai wanda yake da alkawari a wurin (Allah) Mai rahama[2] (88) Suka kuma ce: “(Allah) Mai rahama (wai) yana da ɗa (89) Haƙiƙa kun zo da babban abu (marar daɗin ji) (90) Sama ta kusa ta kece saboda shi (mummunan furucin), ƙasa kuma ta tsage, duwatsu kuma su zube su yi rugu-rugu (91) Saboda sun yi da’awar Allah Yana da ɗa! (92) Bai kuwa dace da (Allah) Mai rahama Ya zama Yana da ɗa ba (93) Ba wani abu da yake cikin sammai da ƙasa face ya zo wa (Allah) Mai rahama a matsayin bawa (94) Lalle Ya kiyaye da su Ya kuma ƙididdige su sosai (95) Kuma dukkansu kowa zai zo masa a ranar alƙiyama shi kaɗai

(1) Watau Allah zai ɗauke shi kacokam lokacin mutuwarsa, ya raba shi da dukiyarsa da ‘ya’yansa da yake taƙama da su.

(2) Watau ya riƙe alƙawarin da ya yi na imani da Allah da manzanninsa.



(96) Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki na gari, to (Allah) Mai rahama zai sanya musu ƙauna[1] (97) To Mun dai saukake shi (Alƙur'ani) da harshenka ne don kawai ka yi wa masu taƙawa albishir da shi, ka kuma gargaɗi mutane masu tsananin jayayya da shi (98) Al'umma nawa Muka hallaka a gabaninsu, shin kana jin ɗuriyar wani daga cikinsu, ko kuwa kana jin 'yar muryarsu?

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَيَجۡعَلُ لَهُمُ
ٱلرَّحۡمَٰنُ وُدّٗا ٩٦ فَإِنَّمَا يَسَّرۡنَٰهُ بِلِسَانِكَ لِتُبَشِّرَ بِهِ
ٱلۡمُتَّقِينَ وَتُنذِرَ بِهِۦ قَوۡمٗا لُّدّٗا ٩٧ وَكَمۡ أَهۡلَكۡنَا قَبۡلَهُم
مِّن قَرۡنٍ هَلۡ تُحِسُّ مِنۡهُم مِّنۡ أَحَدٍ أَوۡ تَسۡمَعُ لَهُمۡ رِكۡزٗا ٩٨

سُورَةُ طٰهٰ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

طه ١ مَآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡقُرۡءَانَ لِتَشۡقَىٰٓ ٢ إِلَّا تَذۡكِرَةٗ
لِّمَن يَخۡشَىٰ ٣ تَنزِيلٗا مِّمَّنۡ خَلَقَ ٱلۡأَرۡضَ وَٱلسَّمَٰوَٰتِ ٱلۡعُلَى ٤
ٱلرَّحۡمَٰنُ عَلَى ٱلۡعَرۡشِ ٱسۡتَوَىٰ ٥ لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي
ٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا وَمَا تَحۡتَ ٱلثَّرَىٰ ٦ وَإِن تَجۡهَرۡ بِٱلۡقَوۡلِ
فَإِنَّهُۥ يَعۡلَمُ ٱلسِّرَّ وَأَخۡفَى ٧ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ لَهُ ٱلۡأَسۡمَآءُ
ٱلۡحُسۡنَىٰ ٨ وَهَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ مُوسَىٰٓ ٩ إِذۡ رَءَا نَارٗا
فَقَالَ لِأَهۡلِهِ ٱمۡكُثُوٓاْ إِنِّيٓ ءَانَسۡتُ نَارٗا لَّعَلِّيٓ ءَاتِيكُم مِّنۡهَا بِقَبَسٍ
أَوۡ أَجِدُ عَلَى ٱلنَّارِ هُدٗى ١٠ فَلَمَّآ أَتَىٰهَا نُودِيَ يَٰمُوسَىٰٓ ١١ إِنِّيٓ
أَنَا۠ رَبُّكَ فَٱخۡلَعۡ نَعۡلَيۡكَ إِنَّكَ بِٱلۡوَادِ ٱلۡمُقَدَّسِ طُوٗى ١٢

Sura Ɗa Ha

(1) Ɗa Ha[2] (2) Ba Mu saukar maka da Alƙur'ani don ka wahala ba (3) Sai don wa'azi ga wanda zai ji tsoron (haɗuwa da Allah) (4) Saukakke ne daga wanda Ya halicci ƙasa da sammai masu ɗaukaka (5) (Allah) Mai rahama, Ya daidaita a kan Al'arshi[3] (6) Abin da yake sammai da ƙasa, da abin da yake tsakaninsu da kuma abin da yake ƙarƙashin ƙasa, (duka) nasa ne (7) Idan kuma ka ɗaga murya da furuci to lalle Shi Yana sane da sirri da abin da ya fi (sirri) ɓuya (8) Allah (Shi ne wanda) babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi; Yana da sunaye mafiya kyau (9) Shin kuwa labarin Musa ya zo maka?(10) Lokacin da ya gano wuta sai ya ce da iyalinsa: "Ku zauna (a nan), lalle ni fa na hangi wuta, (zan je) ko na zo muku da garwashinta ko kuma in sami mai nuna mini (hanya) a wurin wutar." (11) To lokacin da ya zo wurinta (wato wutar), sai aka kira shi (cewa): "Ya Musa (12) "Lalle Ni, Ni ne fa Ubangijinka, sai ka tuɓe takalmanka; lalle kana a tsarkakakken kwarin Ɗuwa ne

(1) Watau zanya farin jininsu a zukatan masoyansa a sama da ƙasa. Shi ma kuma zai ƙaunace su.

(2) Duba Suratul Baƙara, aya ta 1, hashiya ta 8.

(3) Duba Suratul A'arafi, aya ta 54, hashiya ta 126.

وَأَنَا ٱخۡتَرۡتُكَ فَٱسۡتَمِعۡ لِمَا يُوحَىٰٓ ﴿١٣﴾ إِنَّنِيٓ أَنَا ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠
فَٱعۡبُدۡنِي وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ لِذِكۡرِيٓ ﴿١٤﴾ إِنَّ ٱلسَّاعَةَ ءَاتِيَةٌ
أَكَادُ أُخۡفِيهَا لِتُجۡزَىٰ كُلُّ نَفۡسِۭ بِمَا تَسۡعَىٰ ﴿١٥﴾ فَلَا يَصُدَّنَّكَ
عَنۡهَا مَن لَّا يُؤۡمِنُ بِهَا وَٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ فَتَرۡدَىٰ ﴿١٦﴾ وَمَا تِلۡكَ
بِيَمِينِكَ يَٰمُوسَىٰ ﴿١٧﴾ قَالَ هِيَ عَصَايَ أَتَوَكَّؤُاْ عَلَيۡهَا
وَأَهُشُّ بِهَا عَلَىٰ غَنَمِي وَلِيَ فِيهَا مَـَٔارِبُ أُخۡرَىٰ ﴿١٨﴾ قَالَ أَلۡقِهَا
يَٰمُوسَىٰ ﴿١٩﴾ فَأَلۡقَىٰهَا فَإِذَا هِيَ حَيَّةٞ تَسۡعَىٰ ﴿٢٠﴾ قَالَ خُذۡهَا
وَلَا تَخَفۡۖ سَنُعِيدُهَا سِيرَتَهَا ٱلۡأُولَىٰ ﴿٢١﴾ وَٱضۡمُمۡ يَدَكَ
إِلَىٰ جَنَاحِكَ تَخۡرُجۡ بَيۡضَآءَ مِنۡ غَيۡرِ سُوٓءٍ ءَايَةً أُخۡرَىٰ ﴿٢٢﴾ لِنُرِيَكَ
مِنۡ ءَايَٰتِنَا ٱلۡكُبۡرَى ﴿٢٣﴾ ٱذۡهَبۡ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ إِنَّهُۥ طَغَىٰ ﴿٢٤﴾ قَالَ
رَبِّ ٱشۡرَحۡ لِي صَدۡرِي ﴿٢٥﴾ وَيَسِّرۡ لِيٓ أَمۡرِي ﴿٢٦﴾ وَٱحۡلُلۡ عُقۡدَةٗ مِّن
لِّسَانِي ﴿٢٧﴾ يَفۡقَهُواْ قَوۡلِي ﴿٢٨﴾ وَٱجۡعَل لِّي وَزِيرٗا مِّنۡ أَهۡلِي ﴿٢٩﴾ هَٰرُونَ
أَخِي ﴿٣٠﴾ ٱشۡدُدۡ بِهِۦٓ أَزۡرِي ﴿٣١﴾ وَأَشۡرِكۡهُ فِيٓ أَمۡرِي ﴿٣٢﴾ كَيۡ نُسَبِّحَكَ
كَثِيرٗا ﴿٣٣﴾ وَنَذۡكُرَكَ كَثِيرًا ﴿٣٤﴾ إِنَّكَ كُنتَ بِنَا بَصِيرٗا ﴿٣٥﴾ قَالَ قَدۡ
أُوتِيتَ سُؤۡلَكَ يَٰمُوسَىٰ ﴿٣٦﴾ وَلَقَدۡ مَنَنَّا عَلَيۡكَ مَرَّةً أُخۡرَىٰٓ ﴿٣٧﴾

(13) “Kuma Ni Na zaɓe ka (da manzanci), sai ka ji abin da za a yiwo ma wahayi (da shi) (14) “Lalle Ni, Ni ne Allah, babu wani abin bauta sai Ni, to ka bauta mini, kuma ka tsai da salla don tuna Ni

(15) “Lalle alƙiyama za ta zo, ina nufin ɓoye ta ne don a saka wa kowanne rai da irin abin da yake aikatawa (16) “To kada wanda bai yi imani da ita ba ya kuma bi son ransa ya hana ka gaskata ta, sai ka hallaka (17) “Mene ne kuma wancan yake a hannun dama nka ya Musa?”(18) (Musa) ya ce: “Ai sandata ce da nake jingina a kanta, ina kuma kaɗo wa dabbobina ganye da ita, ina kuma da sauran wasu buƙatu game da ita.” (19) (Allah) Ya ce: “Jefar da ita ya Musa.” (20) Sai ya jefar da ita, sai ga ta ta zama macijiya tana ta sauri (21) Ya ce: “Kama ta, kuma kada ka ji tsoro; za Mu mai da ita kamar yadda take a da (22) “Kuma ka haɗa hannunka da kwiɓinka zai fito fari sal ba tare da wata cuta ba; (wannan) wata ayar ce daban (23) “Domin Mu nuna maka irin manya-manyan ayoyinmu (24) “Ka tafi wurin Fir’auna don kuwa lalle ya ƙetare iyaka.”(25) (Musa) ya ce: “Ubangijina Ka buɗe mini ƙirjina[1] (26) “Kuma Ka sauƙaƙa mini lamarina (27) “Ka kuma warware ƙullin da yake a harshena(28) “(Don) su fahimci maganata (29) “Kuma Ka sanya mini waziri daga dangina (30) “(Watau) ɗau’uwana Haruna (31) “Ka ƙarfafa gwiwata da shi (32) “Kuma Ka shigar da shi cikin lamarina[2] (33) “Domin mu tsar“Mu kuma ambace Ka da yawaa tukukumbuke sana (35) “Lalle Kai Ka kasance Kana ganin mu.” (36) (Allah) Ya ce: “Haƙiƙa an ba ka abin da ka tambaya, ya Musa (37) “Haƙiƙa kuma Mun yi ni’ima a gare ka a wani lokaci

(1) Watau ya cire masa in’ina da take damun sa.

(2) Watau shi ma ya ba shi annabta ya aiko su tare.

إِذْ أَوْحَيْنَآ إِلَىٰٓ أُمِّكَ مَا يُوحَىٰٓ ﴿٣٨﴾ أَنِ ٱقْذِفِيهِ فِى ٱلتَّابُوتِ فَٱقْذِفِيهِ
فِى ٱلْيَمِّ فَلْيُلْقِهِ ٱلْيَمُّ بِٱلسَّاحِلِ يَأْخُذْهُ عَدُوٌّ لِّى وَعَدُوٌّ لَّهُۥ ۚ وَأَلْقَيْتُ
عَلَيْكَ مَحَبَّةً مِّنِّى وَلِتُصْنَعَ عَلَىٰ عَيْنِىٓ ﴿٣٩﴾ إِذْ تَمْشِىٓ أُخْتُكَ فَتَقُولُ
هَلْ أَدُلُّكُمْ عَلَىٰ مَن يَكْفُلُهُۥ ۖ فَرَجَعْنَٰكَ إِلَىٰٓ أُمِّكَ كَىْ تَقَرَّ عَيْنُهَا
وَلَا تَحْزَنَ ۚ وَقَتَلْتَ نَفْسًا فَنَجَّيْنَٰكَ مِنَ ٱلْغَمِّ وَفَتَنَّٰكَ فُتُونًا ۚ
فَلَبِثْتَ سِنِينَ فِىٓ أَهْلِ مَدْيَنَ ثُمَّ جِئْتَ عَلَىٰ قَدَرٍ يَٰمُوسَىٰ ﴿٤٠﴾
وَٱصْطَنَعْتُكَ لِنَفْسِى ﴿٤١﴾ ٱذْهَبْ أَنتَ وَأَخُوكَ بِـَٔايَٰتِى وَلَا
تَنِيَا فِى ذِكْرِى ﴿٤٢﴾ ٱذْهَبَآ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ إِنَّهُۥ طَغَىٰ ﴿٤٣﴾ فَقُولَا لَهُۥ قَوْلًا
لَّيِّنًا لَّعَلَّهُۥ يَتَذَكَّرُ أَوْ يَخْشَىٰ ﴿٤٤﴾ قَالَا رَبَّنَآ إِنَّنَا نَخَافُ أَن يَفْرُطَ
عَلَيْنَآ أَوْ أَن يَطْغَىٰ ﴿٤٥﴾ قَالَ لَا تَخَافَآ ۖ إِنَّنِى مَعَكُمَآ أَسْمَعُ وَأَرَىٰ
﴿٤٦﴾ فَأْتِيَاهُ فَقُولَآ إِنَّا رَسُولَا رَبِّكَ فَأَرْسِلْ مَعَنَا بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ
وَلَا تُعَذِّبْهُمْ ۖ قَدْ جِئْنَٰكَ بِـَٔايَةٍ مِّن رَّبِّكَ ۖ وَٱلسَّلَٰمُ عَلَىٰ مَنِ ٱتَّبَعَ
ٱلْهُدَىٰٓ ﴿٤٧﴾ إِنَّا قَدْ أُوحِىَ إِلَيْنَآ أَنَّ ٱلْعَذَابَ عَلَىٰ مَن كَذَّبَ
وَتَوَلَّىٰ ﴿٤٨﴾ قَالَ فَمَن رَّبُّكُمَا يَٰمُوسَىٰ ﴿٤٩﴾ قَالَ رَبُّنَا ٱلَّذِىٓ أَعْطَىٰ
كُلَّ شَىْءٍ خَلْقَهُۥ ثُمَّ هَدَىٰ ﴿٥٠﴾ قَالَ فَمَا بَالُ ٱلْقُرُونِ ٱلْأُولَىٰ ﴿٥١﴾

(38) “Sanda Muka yiwo wahayi ga mahaifiyarka da abin da ake yin wahayi da shi (39) “Cewa, ‘ki saka shi (jinjirin) a cikin akwatu, sannan ki jefa shi cikin kogi, to sai kogin ya jefa shi a gaɓa, sai maƙiyina kuma maƙiyinsa ya ɗauke shi.’ Na kuma sanya maka farin jini daga gare Ni, don kuma a yi tarbiyar ka a gaban idona (40) “Lokacin da ‘yar’uwarka take tafiya tana cewa (da su): ‘Yanzu ba na haɗa ku da wadda za ta raine shi ba?’ Sai Muka komo da kai zuwa ga mahaifiyarka don zuciyarta ta yi sanyi, kada kuma ta yi baƙin ciki. Kuma ka kashe wani mutum[1] sannan Muka tserar da kai daga ukuba, Muka kuma jarrabe ka da jarrabobi daban-daban. Sannan ka zauna shekaru a cikin mutanen Madyana, sannan ka zo (nan) daidai lokacin da Na ƙadarta (maka annabta) ya Musa (41) “Kuma Na zaɓe ka don kaina[2] (42) “Ka tafi kai da ɗan’uwanka da ayoyina, kada kuwa ku sassauta game da ambatona (43) “Ku tafi wurin Fir’auna, don ko lalle ya wuce iyaka (44) “Sai ku gaya masa magana mai taushi, ko watakila zai wa’azantu ko kuma ya ji tsoron (azabar Allah).” (45) (Musa da Haruna) suka ce: “Ya Ubangijinmu, lalle mu muna tsoron ya far mana ko kuma ya wuce iyaka (wajen yi mana uƙuba).” (46) Ya ce: “Kada ku ji tsoro; haƙiƙa Ni ina tare da ku, ina ji kuma ina ganin (komai) (47) “Sai ku tafi wajensa sannan ku ce (da shi): “Lalle mu manzannin Ubangijinka ne, sai ka sakar mana Banu-Isra’ila, kada kuma ka azabtar da su; haƙiƙa mun zo maka da aya daga Ubangijinka; aminci kuwa ya tabbata ga wanda ya bi shiriya (48) “Lalle mu an yi mana wahayi cewa, ita azaba lalle tana nan ga wanda ya ƙaryata ya kuma ba da baya.” (49) (Fir’auna) ya ce: “Wane ne Ubangijin naku ya Musa?” (50) (Musa) ya ce: “Ubangijinmu (Shi ne) Wanda Ya bai wa kowane abu surar halittarsa sannan Ya shiryar (da shi yadda zai yi tasarrufi).”(51) (Fir’auna) ya ce: “To mene ne halin da al’ummun farko suke ciki?”

(1) Shi ne Baƙibɗen da Annabi Musa ya naushe shi ya faɗi nan take ya mutu.

(2) Watau Allah ( ) ya zaɓe shi domin ya yi magana da shi, ya aika shi zuwa Fir’auna da mutanensa.

قَالَ عِلۡمُهَا عِندَ رَبِّي فِي كِتَٰبٖۖ لَّا يَضِلُّ رَبِّي وَلَا يَنسَى ٥٢ ٱلَّذِي
جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ مَهۡدٗا وَسَلَكَ لَكُمۡ فِيهَا سُبُلٗا وَأَنزَلَ مِنَ
ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَخۡرَجۡنَا بِهِۦٓ أَزۡوَٰجٗا مِّن نَّبَاتٖ شَتَّىٰ ٥٣ كُلُواْ
وَٱرۡعَوۡاْ أَنۡعَٰمَكُمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّأُوْلِي ٱلنُّهَىٰ ٥٤ مِنۡهَا
خَلَقۡنَٰكُمۡ وَفِيهَا نُعِيدُكُمۡ وَمِنۡهَا نُخۡرِجُكُمۡ تَارَةً أُخۡرَىٰ ٥٥ وَلَقَدۡ
أَرَيۡنَٰهُ ءَايَٰتِنَا كُلَّهَا فَكَذَّبَ وَأَبَىٰ ٥٦ قَالَ أَجِئۡتَنَا لِتُخۡرِجَنَا
مِنۡ أَرۡضِنَا بِسِحۡرِكَ يَٰمُوسَىٰ ٥٧ فَلَنَأۡتِيَنَّكَ بِسِحۡرٖ مِّثۡلِهِۦ
فَٱجۡعَلۡ بَيۡنَنَا وَبَيۡنَكَ مَوۡعِدٗا لَّا نُخۡلِفُهُۥ نَحۡنُ وَلَآ أَنتَ مَكَانٗا
سُوٗى ٥٨ قَالَ مَوۡعِدُكُمۡ يَوۡمُ ٱلزِّينَةِ وَأَن يُحۡشَرَ ٱلنَّاسُ ضُحٗى
٥٩ فَتَوَلَّىٰ فِرۡعَوۡنُ فَجَمَعَ كَيۡدَهُۥ ثُمَّ أَتَىٰ ٦٠ قَالَ لَهُم
مُّوسَىٰ وَيۡلَكُمۡ لَا تَفۡتَرُواْ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبٗا فَيُسۡحِتَكُم بِعَذَابٖۖ
وَقَدۡ خَابَ مَنِ ٱفۡتَرَىٰ ٦١ فَتَنَٰزَعُوٓاْ أَمۡرَهُم بَيۡنَهُمۡ وَأَسَرُّواْ
ٱلنَّجۡوَىٰ ٦٢ قَالُوٓاْ إِنۡ هَٰذَٰنِ لَسَٰحِرَانِ يُرِيدَانِ أَن يُخۡرِجَاكُم
مِّنۡ أَرۡضِكُم بِسِحۡرِهِمَا وَيَذۡهَبَا بِطَرِيقَتِكُمُ ٱلۡمُثۡلَىٰ ٦٣
فَأَجۡمِعُواْ كَيۡدَكُمۡ ثُمَّ ٱئۡتُواْ صَفّٗاۚ وَقَدۡ أَفۡلَحَ ٱلۡيَوۡمَ مَنِ ٱسۡتَعۡلَىٰ ٦٤

(52) (Musa) ya ce: “Saninsu yana wurin Ubangijina a cikin Lauhul-Mahafuzu; Ubangijina kuma ba Ya kuskure (cikin iliminsa) kuma ba Ya mantuwa
(53) “(Shi ne) Wanda Ya sanya muku ƙasa a shimfiɗe, Ya kuma sanya muku hanyoyi na tafiya cikinta, kuma Ya saukar da ruwa daga sama”, sannan Muka fitar da dangogin shuke-shuke iri-iri da shi (ruwa)
(54) Ku ci (daga tsirran) kuma ku yi kiwon dabbobinku. Lalle a game da wannan akwai ayoyi ga ma’abota hankula

halicce ku, kuma a cikinta za Mu mayar da ku, daga ita kuma za Mu fito da ku a wani karon
(56) Kuma haƙiƙa Mun nuna masa (Fir’auna) ayoyinmu dukkansu, sai ya ƙaryata kuma ya ƙi (ba da gaskiya)
(57) (Fir’auna) ya ce: “Yanzu ka zo mana ne don ka fitar da mu daga ƙasarmu da sihirinka, ya Musa?
(58) “To lalle kuwa za mu zo maka da wani sihirin irinsa; sai ka sanya lokaci na musamman tsakaninmu da kai wanda mu ba za mu saɓa masa ba, kai ma haka, (ya zama) wuri ne tsaka-tsaki”
(59) (Musa) ya ce: “Lokacin (da na sanya) muku shi ne ranar idi, kuma a tattara mutane da hantsi.”
(60) Sai Fir’auna ya juya, sai ya haɗa makircinsa, sannan ya zo (wurin da aka shirya)
(61) Musa ya ce da su: “Kaiconku! Kada fa ku ƙirƙira wa Allah ƙarya, sai Ya hallaka ku da azaba; haƙiƙa kuwa wanda ya ƙirƙira (masa ƙarya) to ya taɓe.”
(62) Sai suka tattauna al’amarinsu a tsakaninsu, suka kuma gana a asirce
(63) Suka ce: “Lalle waɗannan biyun (Musa da Haruna) tabbas matsafa ne, suna so ne su fitar da ku daga ƙasarku da tsafinsu, su kuma tafiyar da kyakkyawar hanyarku (ta rayuwa)
(64) “Sai ku yiwo shiri haɗaɗɗe sannan ku zo sahu-sahu. Haƙiƙa yau kam wanda ya yi nasara ya rabauta!”

قَالُوا۟ يَٰمُوسَىٰٓ إِمَّآ أَن تُلْقِىَ وَإِمَّآ أَن نَّكُونَ أَوَّلَ مَنْ أَلْقَىٰ ﴿٦٥﴾ قَالَ بَلْ
أَلْقُوا۟ ۖ فَإِذَا حِبَالُهُمْ وَعِصِيُّهُمْ يُخَيَّلُ إِلَيْهِ مِن سِحْرِهِمْ أَنَّهَا
تَسْعَىٰ ﴿٦٦﴾ فَأَوْجَسَ فِى نَفْسِهِۦ خِيفَةً مُّوسَىٰ ﴿٦٧﴾ قُلْنَا لَا تَخَفْ إِنَّكَ
أَنتَ ٱلْأَعْلَىٰ ﴿٦٨﴾ وَأَلْقِ مَا فِى يَمِينِكَ تَلْقَفْ مَا صَنَعُوٓا۟ ۖ إِنَّمَا صَنَعُوا۟
كَيْدُ سَٰحِرٍ ۖ وَلَا يُفْلِحُ ٱلسَّاحِرُ حَيْثُ أَتَىٰ ﴿٦٩﴾ فَأُلْقِىَ ٱلسَّحَرَةُ سُجَّدًا
قَالُوٓا۟ ءَامَنَّا بِرَبِّ هَٰرُونَ وَمُوسَىٰ ﴿٧٠﴾ قَالَ ءَامَنتُمْ لَهُۥ قَبْلَ أَنْ ءَاذَنَ
لَكُمْ ۖ إِنَّهُۥ لَكَبِيرُكُمُ ٱلَّذِى عَلَّمَكُمُ ٱلسِّحْرَ ۖ فَلَأُقَطِّعَنَّ أَيْدِيَكُمْ
وَأَرْجُلَكُم مِّنْ خِلَٰفٍ وَلَأُصَلِّبَنَّكُمْ فِى جُذُوعِ ٱلنَّخْلِ وَلَتَعْلَمُنَّ
أَيُّنَآ أَشَدُّ عَذَابًا وَأَبْقَىٰ ﴿٧١﴾ قَالُوا۟ لَن نُّؤْثِرَكَ عَلَىٰ مَا جَآءَنَا مِنَ
ٱلْبَيِّنَٰتِ وَٱلَّذِى فَطَرَنَا ۖ فَٱقْضِ مَآ أَنتَ قَاضٍ ۖ إِنَّمَا تَقْضِى هَٰذِهِ
ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَآ ﴿٧٢﴾ إِنَّآ ءَامَنَّا بِرَبِّنَا لِيَغْفِرَ لَنَا خَطَٰيَٰنَا وَمَآ أَكْرَهْتَنَا
عَلَيْهِ مِنَ ٱلسِّحْرِ ۗ وَٱللَّهُ خَيْرٌ وَأَبْقَىٰٓ ﴿٧٣﴾ إِنَّهُۥ مَن يَأْتِ رَبَّهُۥ مُجْرِمًا
فَإِنَّ لَهُۥ جَهَنَّمَ لَا يَمُوتُ فِيهَا وَلَا يَحْيَىٰ ﴿٧٤﴾ وَمَن يَأْتِهِۦ مُؤْمِنًا قَدْ
عَمِلَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَأُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلدَّرَجَٰتُ ٱلْعُلَىٰ ﴿٧٥﴾ جَنَّٰتُ عَدْنٍ
تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۚ وَذَٰلِكَ جَزَٰٓؤُا۟ مَن تَزَكَّىٰ ﴿٧٦﴾

**(65) Suka ce: “Ya Musa, ko dai ka jefa (naka) ko kuma mu mu fara jefa (namu).”
(66) Ya ce: “A’a, ku (fara) jefawa.” To saboda sihirinsu sai ga igiyoyinsu da sandunansu ana suranta masa cewa su (macizai ne) suna sauri (67) Sai Musa ya ɓoye (wani abu) na tsoro a ransa (68) Muka ce: “Kada ka ji tsoro, lalle kai kake da rinjaye (69) “Kuma ka jefar da abin da yake hannunka na dama, za ta haɗiye abin da suka aikata; lalle abin da suka aikata makircin matsafi ne; matsafi kuwa ba ya rabauta duk ta inda ya zo.” (70) Sai matsafan suka faɗi suna sujjada[1] suka ce: “Mun yi imani da Ubangijin Haruna da Musa!” (71) (Fir’auna) ya ce: “Yanzu kwa yi imani da shi tun kafin in yi muku izini? Lalle shi ne babbanku wanda ya koya muku tsafi; to lalle zan yayyanke hannayenku da ƙafafuwanku a tarnaƙe (wato hannun dama da ƙafar hagu), kuma tabbas zan gicciye ku a kan kututturen dabino, lalle kuma tabbas za ku san wane ne tsakanin ni da shi wanda ya fi tsananin azaba kuma ta fi ɗorewa (72) Suka ce: “Ba za mu fifita ka ba a kan abin da ya zo mana na (ayoyi) mabayyana, da kuma a kan wanda Ya halicce mu. Sai ka hukunta duk abin da za ka hukunta; za ka yi hukunci ne kawai a wannnan rayuwar ta duniya (73) “Lalle mu kam mun yi imani da Ubangijinmu don Ya gafarta mana laifukanmu da kuma abin da ka tilasta mu a kansa na tsafi. Allah kuwa Shi ne Mafi alherin (sakamako), kuma Shi ne Mafi dawwamar (azaba).” (74) Lalle duk wanda ya zo wa Ubangijinsa yana mai babban laifi[2] to lalle yana da (sakamakon) Jahannama, ba zai mutu a cikinta ba, ba kuma zai rayu ba (rayuwa mai daɗi) (75) Wanda kuwa ya zo masa yana mumini ya zamana ya yi aiki na gari, to waɗannan suna da (sakamakon samun) darajoji maɗaukaka (76) (Watau) gidajen Aljanna na dawwama waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, masu dawwama ne a cikinsu. Wannan kuwa shi ne sakamakon wanda ya tsarkaka (daga saɓo)**

(1) Watau bayan sun fahimci cewa abin da Musa ( ) ya zo da shi ba tsafi ba ne, wani abu ne daga Allah.

(2) Watau kafirce wa Allah da haɗa wani da shi a wajen bauta.

وَلَقَدْ أَوْحَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنْ أَسْرِ بِعِبَادِى فَٱضْرِبْ لَهُمْ طَرِيقًا
فِى ٱلْبَحْرِ يَبَسًا لَّا تَخَٰفُ دَرَكًا وَلَا تَخْشَىٰ ﴿٧٧﴾ فَأَتْبَعَهُمْ فِرْعَوْنُ
بِجُنُودِهِۦ فَغَشِيَهُم مِّنَ ٱلْيَمِّ مَا غَشِيَهُمْ ﴿٧٨﴾ وَأَضَلَّ فِرْعَوْنُ قَوْمَهُۥ
وَمَا هَدَىٰ ﴿٧٩﴾ يَٰبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ قَدْ أَنجَيْنَٰكُم مِّنْ عَدُوِّكُمْ وَوَٰعَدْنَٰكُمْ
جَانِبَ ٱلطُّورِ ٱلْأَيْمَنَ وَنَزَّلْنَا عَلَيْكُمُ ٱلْمَنَّ وَٱلسَّلْوَىٰ ﴿٨٠﴾ كُلُوا۟ مِن
طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقْنَٰكُمْ وَلَا تَطْغَوْا۟ فِيهِ فَيَحِلَّ عَلَيْكُمْ غَضَبِى ۖ
وَمَن يَحْلِلْ عَلَيْهِ غَضَبِى فَقَدْ هَوَىٰ ﴿٨١﴾ وَإِنِّى لَغَفَّارٌ لِّمَن تَابَ
وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحًا ثُمَّ ٱهْتَدَىٰ ﴿٨٢﴾ ۞ وَمَآ أَعْجَلَكَ عَن
قَوْمِكَ يَٰمُوسَىٰ ﴿٨٣﴾ قَالَ هُمْ أُو۟لَآءِ عَلَىٰٓ أَثَرِى وَعَجِلْتُ إِلَيْكَ
رَبِّ لِتَرْضَىٰ ﴿٨٤﴾ قَالَ فَإِنَّا قَدْ فَتَنَّا قَوْمَكَ مِنۢ بَعْدِكَ وَأَضَلَّهُمُ
ٱلسَّامِرِىُّ ﴿٨٥﴾ فَرَجَعَ مُوسَىٰٓ إِلَىٰ قَوْمِهِۦ غَضْبَٰنَ أَسِفًا ۖ قَالَ
يَٰقَوْمِ أَلَمْ يَعِدْكُمْ رَبُّكُمْ وَعْدًا حَسَنًا ۚ أَفَطَالَ عَلَيْكُمُ ٱلْعَهْدُ
أَمْ أَرَدتُّمْ أَن يَحِلَّ عَلَيْكُمْ غَضَبٌ مِّن رَّبِّكُمْ فَأَخْلَفْتُم
مَّوْعِدِى ﴿٨٦﴾ قَالُوا۟ مَآ أَخْلَفْنَا مَوْعِدَكَ بِمَلْكِنَا وَلَٰكِنَّا حُمِّلْنَآ
أَوْزَارًا مِّن زِينَةِ ٱلْقَوْمِ فَقَذَفْنَٰهَا فَكَذَٰلِكَ أَلْقَى ٱلسَّامِرِىُّ ﴿٨٧﴾

(77) Haƙiƙa kuma Mun yi wa Musa wahayi cewa: “Ka tafi da bayina cikin dare sannan ka keta musu hanya ƙeƙasasshiya a cikin kogi, ba za ka ji tsoron riskar (Fir’auna da jama’arsa) ba, kuma ba za ka ji tsoron (nutsewa) ba.” (78) Sai Fir’auna ya bi su shi da rundunarsa sai abin da ya haɗe su na ruwan kogi ya haɗiye su (suka hallaka kakaf)! (79) Fir’auna kuma ya ɓatar da mutanensa bai kuma shiryar (da su) ba (80) Ya ku Banu-Isra’ila, haƙiƙa Mun tserar da ku daga maƙiyinku, (watau Fir’auna) Muka kuma yi muku alƙawarin (ganawa) a ɓarin dama na dutsen Ɗuri[1], Muka kuma saukar muku da darɓa da kuma (gasassun tsuntsayen) salwa (81) Ku ci daga daɗaɗan abin da Muka arzuta ku da shi (na halal), kada kuwa ku ƙetare shi (zuwa haramun), sai fushina ya faɗa muku; wanda kuwa fushina ya faɗa masa, to haƙiƙa ya hallaka (82) Lalle Ni kuma Mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba kuma ya yi aiki na gari sannan ya (tabbata bisa) shiriya (83) Kuma me ya sa ka gaggawar barin mutanenka, ya Musa? (84) (Musa) ya ce: “Su waɗannan (mutane nawa) ai za su biyo bayana ne (ba da jimawa ba), na kuwa yi gaggawa ne zuwa gare Ka ya Ubangijina don neman yardarka.” (85) (Allah) ya ce: “To lalle Mun jarrabi mutanenka a bayanka, Samiri kuma ya ɓatar da su[2].” (86) Sai Musa ya komo zuwa ga mutanensa cike da fushi da baƙin ciki. Ya ce: “Ya ku mutanena, yanzu Ubangijinku bai yi muku kyakkyawan alƙawari ba[3]? Ko kuwa lokacin alƙawarin ne ya yi muku tsawo? Ko kuwa kuna so ne fushin Ubangijinku ya saukar muku, shi ne sai kuka saɓa alƙawarin (da muka yi na ku tabbata bisa imani)?” (87) Suka ce: “Ba mu saɓa alƙawarinka da zaɓin kanmu ba, sai dai mu an ɗora mana kayayyakin nauyi ne na ababan adon mutane (Kibɗawa), sai muka jefa su (a cikin wuta), sannan Samiri ya jefa (nasa) kamar yadda (muka yi).”

(1) Watau Allah ( ) ya yi musu alƙawarin ganawa da Annabi Musa ( ), domin yin magana da shi da ba shi littafin Attaura mai ƙunshe da shiriya a gare su.

(2) Samiri, wani munafuki ne a cikin Banu Isra’ila wanda ya ja su zuwa ga bautar ɗan maraƙi.

(3) Alƙawari na cewa zai saukar musu da littafin Attaura, ya kuma shigar da su Aljjanna idan sun mutu.

فَأَخْرَجَ لَهُمْ عِجْلًا جَسَدًا لَّهُۥ خُوَارٌ فَقَالُوا۟ هَٰذَآ إِلَٰهُكُمْ
وَإِلَٰهُ مُوسَىٰ فَنَسِىَ ﴿٨٨﴾ أَفَلَا يَرَوْنَ أَلَّا يَرْجِعُ إِلَيْهِمْ قَوْلًا
وَلَا يَمْلِكُ لَهُمْ ضَرًّا وَلَا نَفْعًا ﴿٨٩﴾ وَلَقَدْ قَالَ لَهُمْ هَٰرُونُ
مِن قَبْلُ يَٰقَوْمِ إِنَّمَا فُتِنتُم بِهِۦ ۖ وَإِنَّ رَبَّكُمُ ٱلرَّحْمَٰنُ فَٱتَّبِعُونِى
وَأَطِيعُوٓا۟ أَمْرِى ﴿٩٠﴾ قَالُوا۟ لَن نَّبْرَحَ عَلَيْهِ عَٰكِفِينَ حَتَّىٰ يَرْجِعَ
إِلَيْنَا مُوسَىٰ ﴿٩١﴾ قَالَ يَٰهَٰرُونُ مَا مَنَعَكَ إِذْ رَأَيْتَهُمْ ضَلُّوٓا۟ ﴿٩٢﴾
أَلَّا تَتَّبِعَنِ ۖ أَفَعَصَيْتَ أَمْرِى ﴿٩٣﴾ قَالَ يَبْنَؤُمَّ لَا تَأْخُذْ بِلِحْيَتِى
وَلَا بِرَأْسِىٓ ۖ إِنِّى خَشِيتُ أَن تَقُولَ فَرَّقْتَ بَيْنَ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ
وَلَمْ تَرْقُبْ قَوْلِى ﴿٩٤﴾ قَالَ فَمَا خَطْبُكَ يَٰسَٰمِرِىُّ ﴿٩٥﴾ قَالَ
بَصُرْتُ بِمَا لَمْ يَبْصُرُوا۟ بِهِۦ فَقَبَضْتُ قَبْضَةً مِّنْ أَثَرِ
ٱلرَّسُولِ فَنَبَذْتُهَا وَكَذَٰلِكَ سَوَّلَتْ لِى نَفْسِى ﴿٩٦﴾ قَالَ
فَٱذْهَبْ فَإِنَّ لَكَ فِى ٱلْحَيَوٰةِ أَن تَقُولَ لَا مِسَاسَ ۖ وَإِنَّ لَكَ
مَوْعِدًا لَّن تُخْلَفَهُۥ ۖ وَٱنظُرْ إِلَىٰٓ إِلَٰهِكَ ٱلَّذِى ظَلْتَ عَلَيْهِ
عَاكِفًا ۖ لَّنُحَرِّقَنَّهُۥ ثُمَّ لَنَنسِفَنَّهُۥ فِى ٱلْيَمِّ نَسْفًا ﴿٩٧﴾ إِنَّمَآ
إِلَٰهُكُمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِى لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۚ وَسِعَ كُلَّ شَىْءٍ عِلْمًا ﴿٩٨﴾

(88) To sai ya fitar musu da ɗan maraƙi jika-jika mai kuka, sai suka ce(1): “Wannan ubangijinku ne kuma ubangijin Musa, amma sai ya manta (da yana nan).” (89) Yanzu ba sa gani cewa (maraƙin) ba ya mayar musu da magana, kuma ba ya mallakar wata cuta ko amfani gare su? (90) Alhali kuwa haƙiƙa Haruna ya faɗa musu tun da wuri cewa: “Ya ku mutanena, an jarrabe ku da shi ne kawai, kuma lalle Ubangijinku (na gaskiya) Shi ne Arrahamanu, sai ku bi ni kuma ku bi umarnina.” (91) Suka ce: “Ba za mu gushe masa ba har sai Musa ya dawo mana.” (92) (Musa) ya ce: “Ya Haruna, me ya hana ka lokacin da ka gan su sun ɓace? (93) “Ka bi ni (don ka sanar da ni)? Ko kuwa ka saɓa umarnina ne?” (94) (Haruna) ya ce: “Ya ɗan’ummata, kada ka kama mini gemuna, da kuma (gashin) kaina; lalle ni na ji tsoron ka ce (da ni): ‘Ka rarraba kan Banu-Isra’ila, ba ka kuma kiyaye maganata ba.’” (95) (Musa) ya ce: “Mene ne lamarinka, ya Samiri?” (96) Ya ce: “Na ga abin da ba su gani ba ne(1), sai na ɗebi ɗanƙi daga gurbin (ƙasar) sawun (goɗiyar) Manzon (wato Jibrilu) sannan na watsa ta (a kan ɗan maraƙin). Kamar haka kuwa raina ya ƙawata mini.” (97) (Annabi Musa) ya ce: “To sai ka tafi, amma ka tabbatar cewa (sakamakonka) a rayuwar (da za ka yi) shi ne ka riƙa cewa ‘la misasa’, (watau ba za ka taɓu ba kuma ba za ka taɓa kowa ba)(2); kuma lalle kana da ƙayyadajjen lokaci wanda ba za a saɓa maka ba; kuma ka dubi ubangijin naka wanda ka duƙufa a kansa kana bauta; lalle za mu ƙona shi sannan tabbas za mu shefkar da shi cikin kogi.” (98) Abin bautarku kawai shi ne Allah wanda babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi. Ya yalwaci komai da iliminsa

(1) Watau wasu fitinannu daga cikin Banu Isra’ila suka faɗi wannan magana.

(2) Watau ba zai iya gauraya da mutane ba; don ba zai iya taɓa kowa ba, ba kuma wanda zai iya taɓa jikinsa.

كَذَٰلِكَ نَقُصُّ عَلَيْكَ مِنْ أَنۢبَآءِ مَا قَدْ سَبَقَ ۚ وَقَدْ ءَاتَيْنَٰكَ مِن لَّدُنَّا
ذِكْرًا ﴿٩٩﴾ مَّنْ أَعْرَضَ عَنْهُ فَإِنَّهُۥ يَحْمِلُ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ وِزْرًا
﴿١٠٠﴾ خَٰلِدِينَ فِيهِ ۖ وَسَآءَ لَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ حِمْلًا ﴿١٠١﴾ يَوْمَ يُنفَخُ
فِى ٱلصُّورِ ۚ وَنَحْشُرُ ٱلْمُجْرِمِينَ يَوْمَئِذٍ زُرْقًا ﴿١٠٢﴾ يَتَخَٰفَتُونَ
بَيْنَهُمْ إِن لَّبِثْتُمْ إِلَّا عَشْرًا ﴿١٠٣﴾ نَّحْنُ أَعْلَمُ بِمَا يَقُولُونَ إِذْ يَقُولُ
أَمْثَلُهُمْ طَرِيقَةً إِن لَّبِثْتُمْ إِلَّا يَوْمًا ﴿١٠٤﴾ وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْجِبَالِ
فَقُلْ يَنسِفُهَا رَبِّى نَسْفًا ﴿١٠٥﴾ فَيَذَرُهَا قَاعًا صَفْصَفًا ﴿١٠٦﴾
لَّا تَرَىٰ فِيهَا عِوَجًا وَلَآ أَمْتًا ﴿١٠٧﴾ يَوْمَئِذٍ يَتَّبِعُونَ ٱلدَّاعِىَ
لَا عِوَجَ لَهُۥ ۖ وَخَشَعَتِ ٱلْأَصْوَاتُ لِلرَّحْمَٰنِ فَلَا تَسْمَعُ إِلَّا هَمْسًا
﴿١٠٨﴾ يَوْمَئِذٍ لَّا تَنفَعُ ٱلشَّفَٰعَةُ إِلَّا مَنْ أَذِنَ لَهُ ٱلرَّحْمَٰنُ وَرَضِىَ لَهُۥ
قَوْلًا ﴿١٠٩﴾ يَعْلَمُ مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ وَلَا يُحِيطُونَ بِهِۦ
عِلْمًا ﴿١١٠﴾ ۞ وَعَنَتِ ٱلْوُجُوهُ لِلْحَىِّ ٱلْقَيُّومِ ۖ وَقَدْ خَابَ مَنْ حَمَلَ
ظُلْمًا ﴿١١١﴾ وَمَن يَعْمَلْ مِنَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَلَا يَخَافُ
ظُلْمًا وَلَا هَضْمًا ﴿١١٢﴾ وَكَذَٰلِكَ أَنزَلْنَٰهُ قُرْءَانًا عَرَبِيًّا وَصَرَّفْنَا
فِيهِ مِنَ ٱلْوَعِيدِ لَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ أَوْ يُحْدِثُ لَهُمْ ذِكْرًا ﴿١١٣﴾

(99) Kamar haka ne Muke ba ka labari daga labaran abubuwan da suka riga suka wuce. Haƙiƙa kuwa Mun ba ka Alƙur'ani daga wajenmu (100) Duk wanda ya bijire masa to lalle zai ɗauki nauyin zunubi a ranar alƙiyama (101) (Suna) madawwama a cikinsa (zunubin); kayan (zunubi) kuwa ya munana a gare su ranar alƙiyama (102) (Ita ce) ranar da za a busa ƙaho. Kuma Mu tayar da kafirai a wannan ranar idanuwansu jawur(1)

(103) Suna raɗa a tsakaninsu (suna cewa): "Ba ku zauna (a ƙaburburanku) ba face (kwana) goma."

suke faɗi lokacin da wanda ya fi tunani daga cikinsu yake cewa: "Ba ku zauna ba face rana guda."

(105) Suna kuma tambayar ka game da duwatsu, to ka ce (da su): "Ubangijina zai niƙe su tilis

(106) "Sannan Ya bar ta (wato ƙasar) fili fetal

(107) "Ba za ka ga wani kwari ko tudu a kanta ba."

(108) A wannan rana ne za su bi mai kira (zuwa matattara), ba mai baudɗe masa; kuma (duk) muryoyi su yi ƙasa-ƙasa saboda (girman Allah) Mai rahama, sannan ba za ka ji (komai) ba sai raɗa

(109) A wannan ranar ceto ba ya amfani sai ga wanda (Allah) Mai rahama Ya yi wa izini, kuma Ya yarda da maganarsa

(110) (Allah) Yana sane da abin da yake gaba gare su (na ranar alƙiyama) da kuma abin da yake bayansu (na ayyukan da suka yi a duniya), su kuwa ba za su kewaye da saninsa ba

(111) Kuma dukkanin fuskoki suka ƙasƙanta ga (Allah) Rayayye, Tsayayye (da Zatinsa). Haƙiƙa kuma duk wanda ya yo dakon zalunci ya taɓe

(112) Duk kuma wanda yake yin aiki na gari alhali kuwa shi mumini ne, to ba zai ji tsoron zalunci ba ko kuma ƙwauro

(113) Kuma kamar haka Muka saukar da shi (Alƙur'ani) Balarabe (watau da harshen Larabci), Muka kuma sarrafa ayoyin gargaɗi a cikinsa don su kiyaye dokokin (Allah) ko kuma ya sa su su wa'azantu

(1) Watau saboda tsananin tsoro da fargaba.

فَتَعَٰلَى ٱللَّهُ ٱلْمَلِكُ ٱلْحَقُّ ۗ وَلَا تَعْجَلْ بِٱلْقُرْءَانِ مِن قَبْلِ أَن
يُقْضَىٰٓ إِلَيْكَ وَحْيُهُۥ ۖ وَقُل رَّبِّ زِدْنِى عِلْمًا ﴿١١٤﴾ وَلَقَدْ عَهِدْنَآ
إِلَىٰٓ ءَادَمَ مِن قَبْلُ فَنَسِىَ وَلَمْ نَجِدْ لَهُۥ عَزْمًا ﴿١١٥﴾ وَإِذْ قُلْنَا
لِلْمَلَٰٓئِكَةِ ٱسْجُدُوا۟ لِءَادَمَ فَسَجَدُوٓا۟ إِلَّآ إِبْلِيسَ أَبَىٰ ﴿١١٦﴾
فَقُلْنَا يَٰٓـَٔادَمُ إِنَّ هَٰذَا عَدُوٌّ لَّكَ وَلِزَوْجِكَ فَلَا يُخْرِجَنَّكُمَا
مِنَ ٱلْجَنَّةِ فَتَشْقَىٰٓ ﴿١١٧﴾ إِنَّ لَكَ أَلَّا تَجُوعَ فِيهَا وَلَا تَعْرَىٰ
﴿١١٨﴾ وَأَنَّكَ لَا تَظْمَؤُا۟ فِيهَا وَلَا تَضْحَىٰ ﴿١١٩﴾ فَوَسْوَسَ إِلَيْهِ
ٱلشَّيْطَٰنُ قَالَ يَٰٓـَٔادَمُ هَلْ أَدُلُّكَ عَلَىٰ شَجَرَةِ ٱلْخُلْدِ وَمُلْكٍ
لَّا يَبْلَىٰ ﴿١٢٠﴾ فَأَكَلَا مِنْهَا فَبَدَتْ لَهُمَا سَوْءَٰتُهُمَا وَطَفِقَا
يَخْصِفَانِ عَلَيْهِمَا مِن وَرَقِ ٱلْجَنَّةِ ۚ وَعَصَىٰٓ ءَادَمُ رَبَّهُۥ فَغَوَىٰ
﴿١٢١﴾ ثُمَّ ٱجْتَبَٰهُ رَبُّهُۥ فَتَابَ عَلَيْهِ وَهَدَىٰ ﴿١٢٢﴾ قَالَ ٱهْبِطَا مِنْهَا
جَمِيعًۢا ۖ بَعْضُكُمْ لِبَعْضٍ عَدُوٌّ ۖ فَإِمَّا يَأْتِيَنَّكُم مِّنِّى هُدًى
فَمَنِ ٱتَّبَعَ هُدَاىَ فَلَا يَضِلُّ وَلَا يَشْقَىٰ ﴿١٢٣﴾ وَمَنْ أَعْرَضَ
عَن ذِكْرِى فَإِنَّ لَهُۥ مَعِيشَةً ضَنكًا وَنَحْشُرُهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ
أَعْمَىٰ ﴿١٢٤﴾ قَالَ رَبِّ لِمَ حَشَرْتَنِىٓ أَعْمَىٰ وَقَدْ كُنتُ بَصِيرًا ﴿١٢٥﴾

(114) Kuma fa Allah Sarki na gaskiya Ya ɗaukaka (daga maganganun kafirai). Kada kuma ka yi garaje da (karatun) Alkur'ani tun kafin a gama yi maka wahayinsa, kuma ka ce: "Ubangiji Ka ƙara min ilimi."
(115) Kuma haƙiƙa Mun yi alkawari da Adamu tun da farko (cewa kada ya ci itaciyar da aka hana shi), sai ya manta, sai ba Mu same shi da ƙarfin ƙuduri ba
(116) Kuma (ka tuna) lokacin da Muka ce da mala'iku: "Ku yi sujjada ga Adamu" sai suka yi sujjadar sai Iblis ne kawai ya ƙi
(117) Sannan Muka ce: "Ya Adamu, lalle wannan maƙiyinka ne kai da matarka, to kada (ku yarda) ya fitar da ku daga Aljanna, sai ka wahala
(118) "Lalle (Allah) Ya yi maka alkawarin ba za ka ji yunwa ba a cikinta, kuma ba za ka yi tsiraici ba
(119) "Kuma lalle kai ba za ka ji ƙishi ba a cikinta, kuma ba za ka ji zafin rana ba."
(120) Sai Shaiɗan ya yi masa waswasi ya ce: "Ya Adamu, yanzu ba na nuna maka wata bishiya ta dawwama da kuma mulki wanda ba zai ƙare ba?"
(121) Sai suka ci wani abu daga gare ta, sai ga tsiraicinsu ya bayyana gare su, sai suka riƙa lulluɓe (jikinsu) da ganyen Aljanna. Kuma Adamu ya saɓa wa Ubangijinsa ya bar shiriya
(122) Sannan Ubangijinsa Ya zaɓe shi, sai Ya yafe masa Ya kuma shirye (shi)
(123) (Allah) Ya ce (da Adamu da Hauwa'u): "Ku sauka daga gare ta (Aljannar) gaba ɗayanku, sashinku ya dinga gaba da sashi; sannan idan shiriya ta zo muku daga gare Ni, to duk wanda ya bi shiriyata ba zai taɓe ba, kuma ba zai wahala ba
(124) "Wanda kuma ya bijire wa Alkur'ani to lalle zai yi rayuwa mai ƙunci, kuma Mu tashe shi makaho ranar alkiyama."
(125) Zai ce: "Ubangijina me ya sa Ka tashe ni makaho, alhali kuwa na kasance mai gani?"

قَالَ كَذَٰلِكَ أَتَتْكَ ءَايَٰتُنَا فَنَسِيتَهَا ۖ وَكَذَٰلِكَ ٱلْيَوْمَ تُنسَىٰ ﴿١٢٦﴾
وَكَذَٰلِكَ نَجْزِى مَنْ أَسْرَفَ وَلَمْ يُؤْمِنۢ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِۦ ۚ وَلَعَذَابُ ٱلْءَاخِرَةِ
أَشَدُّ وَأَبْقَىٰٓ ﴿١٢٧﴾ أَفَلَمْ يَهْدِ لَهُمْ كَمْ أَهْلَكْنَا قَبْلَهُم مِّنَ ٱلْقُرُونِ
يَمْشُونَ فِى مَسَٰكِنِهِمْ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَٰتٍ لِّأُو۟لِى ٱلنُّهَىٰ ﴿١٢٨﴾
وَلَوْلَا كَلِمَةٌ سَبَقَتْ مِن رَّبِّكَ لَكَانَ لِزَامًا وَأَجَلٌ مُّسَمًّى ﴿١٢٩﴾
فَٱصْبِرْ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ قَبْلَ طُلُوعِ ٱلشَّمْسِ
وَقَبْلَ غُرُوبِهَا ۖ وَمِنْ ءَانَآئِ ٱلَّيْلِ فَسَبِّحْ وَأَطْرَافَ ٱلنَّهَارِ لَعَلَّكَ
تَرْضَىٰ ﴿١٣٠﴾ وَلَا تَمُدَّنَّ عَيْنَيْكَ إِلَىٰ مَا مَتَّعْنَا بِهِۦٓ أَزْوَٰجًا مِّنْهُمْ زَهْرَةَ
ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا لِنَفْتِنَهُمْ فِيهِ ۚ وَرِزْقُ رَبِّكَ خَيْرٌ وَأَبْقَىٰ ﴿١٣١﴾ وَأْمُرْ أَهْلَكَ
بِٱلصَّلَوٰةِ وَٱصْطَبِرْ عَلَيْهَا ۖ لَا نَسْـَٔلُكَ رِزْقًا ۖ نَّحْنُ نَرْزُقُكَ ۗ وَٱلْعَٰقِبَةُ
لِلتَّقْوَىٰ ﴿١٣٢﴾ وَقَالُوا۟ لَوْلَا يَأْتِينَا بِـَٔايَةٍ مِّن رَّبِّهِۦٓ ۚ أَوَلَمْ تَأْتِهِم
بَيِّنَةُ مَا فِى ٱلصُّحُفِ ٱلْأُولَىٰ ﴿١٣٣﴾ وَلَوْ أَنَّآ أَهْلَكْنَٰهُم بِعَذَابٍ
مِّن قَبْلِهِۦ لَقَالُوا۟ رَبَّنَا لَوْلَآ أَرْسَلْتَ إِلَيْنَا رَسُولًا فَنَتَّبِعَ
ءَايَٰتِكَ مِن قَبْلِ أَن نَّذِلَّ وَنَخْزَىٰ ﴿١٣٤﴾ قُلْ كُلٌّ مُّتَرَبِّصٌ فَتَرَبَّصُوا۟ ۖ
فَسَتَعْلَمُونَ مَنْ أَصْحَٰبُ ٱلصِّرَٰطِ ٱلسَّوِىِّ وَمَنِ ٱهْتَدَىٰ ﴿١٣٥﴾

(126) (Allah) Ya ce: “Kamar haka ne ayoyinmu suka zo maka sai ka manta su, to kamar haka kuwa (kai ma) za a manta da kai a yau.”
(127) Kamar haka Muke saka wa (duk) wanda ya yi ɓarna kuma bai yi imani da ayoyin Ubangijinsa ba. Kuma azabar lahira tabbas ta fi tsanani ta kuma fi dawwama
(128) Yanzu (mutanen Makka) ba su gane cewa al’ummu nawa muka hallaka a gabaninsu ba waɗanda suna wucewa ta gidajensu? Lalle a game da wannan akwai ayoyi ga ma’abota hankali
(129) Ba don kuwa wata kalma da ta rigaya daga Ubangijinka ba[1], da kuma wani wa’adi ƙayyadajje[2], to da (azaba) ta zama dole (a kansu tun a duniya)
(130) Sai ka yi haƙuri a kan abin da suke faɗa, kuma ka yi tasbihi da godiyar Ubangijinka kafin hudowar rana, da kuma gabanin faɗuwarta; a (wasu) lokatai na dare kuma ka yi tasbihi, da kuma gefukan wuni don (a saka maka da abin da) za ka yarda
(131) Kada kuma ka zura idanuwanka a kan dangogin daɗin da Muka jiyar da wasu daga cikinsu, na adon rayuwar duniya ne don Mu jarrabe su da shi. Arzikin Ubangijinka kuwa (shi) ya fi alheri ya kuma fi dawwama
(132) Ka kuma umarci iyalinka da (tsai da) salla, kuma ka dawwama a kanta; ba Ma neman ka arzuta (kanka da iyalinka); Mu ne za Mu arzuta ka. Kyakkyawan ƙarshe kuwa yana ga masu taƙawa
(133) Suka kuma ce: “Me ya sa bai zo mana da wata aya daga Ubangijinsa ba?” Yanzu hujjar abin da yake cikin littattafan farko ba ta zo musu ba (wato Alƙur’ani)?
(134) In da a ce Mun hallaka su ne da azaba tun gabaninsa (wato Annabi Muhammadu), to da sun ce: “Ubangijinmu, me ya sa ba Ka aiko mana da wani manzo ba sai mu bi ayoyinka tun kafin mu ƙasƙanta mu kuma wulaƙanta?”
(135) Ka ce (da su): “Kowanne (ni da ku) mai sauraro ne, sai ku saurara; to ba da daɗewa ba za ku san su wane ne ma’abota hanya madaidaiciya, kuma su wane ne suke kan shiriya.”

(1) Watau alƙawari na cewa ba zai hallakar da kowa ba har sai ya tsayar masa da hujja.

(2) Watau ajali na rayuwa da ya riga ya ƙayyade wa kowa a duniya.

Sura Anbiya

سُورَةُ الأَنبِيَاءِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

اقْتَرَبَ لِلنَّاسِ حِسَابُهُمْ وَهُمْ فِي غَفْلَةٍ مُّعْرِضُونَ ﴿١﴾
مَا يَأْتِيهِم مِّن ذِكْرٍ مِّن رَّبِّهِم مُّحْدَثٍ إِلَّا اسْتَمَعُوهُ وَهُمْ
يَلْعَبُونَ ﴿٢﴾ لَاهِيَةً قُلُوبُهُمْ ۗ وَأَسَرُّوا النَّجْوَى الَّذِينَ
ظَلَمُوا هَلْ هَٰذَا إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ ۖ أَفَتَأْتُونَ السِّحْرَ وَأَنتُمْ
تُبْصِرُونَ ﴿٣﴾ قَالَ رَبِّي يَعْلَمُ الْقَوْلَ فِي السَّمَاءِ وَالْأَرْضِ ۖ
وَهُوَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ ﴿٤﴾ بَلْ قَالُوا أَضْغَاثُ أَحْلَامٍ بَلِ
افْتَرَاهُ بَلْ هُوَ شَاعِرٌ فَلْيَأْتِنَا بِآيَةٍ كَمَا أُرْسِلَ الْأَوَّلُونَ
﴿٥﴾ مَا آمَنَتْ قَبْلَهُم مِّن قَرْيَةٍ أَهْلَكْنَاهَا ۖ أَفَهُمْ يُؤْمِنُونَ
﴿٦﴾ وَمَا أَرْسَلْنَا قَبْلَكَ إِلَّا رِجَالًا نُّوحِي إِلَيْهِمْ ۖ فَاسْأَلُوا أَهْلَ
الذِّكْرِ إِن كُنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿٧﴾ وَمَا جَعَلْنَاهُمْ جَسَدًا
لَّا يَأْكُلُونَ الطَّعَامَ وَمَا كَانُوا خَالِدِينَ ﴿٨﴾ ثُمَّ صَدَقْنَاهُمُ
الْوَعْدَ فَأَنجَيْنَاهُمْ وَمَن نَّشَاءُ وَأَهْلَكْنَا الْمُسْرِفِينَ ﴿٩﴾
لَقَدْ أَنزَلْنَا إِلَيْكُمْ كِتَابًا فِيهِ ذِكْرُكُمْ ۖ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿١٠﴾

(1) Lokacin yi wa mutane hisabi ya kusanto, alhali suna cikin gafala (suna) masu bijirewa
(2) Ba wata tunatarwa sabowa (wato Alkur'ani) da za ta zo musu daga Ubangijinsu face sai sun saurare ta suna masu wasa
(3) Zukatansu suna cikin gafala. Waɗanda suka yi zalunci kuma suka ɓoye abin da suka tattauna (na cewa): "Wannan ba wani ne in ban da mutum kamarku; yanzu kwa riƙa bin sihiri alhali kuwa ku kuna gani?"
(4) Ya ce: "Ubangijina Yana sane da (kowace) magana a cikin sammai da ƙasa; Shi kuwa Mai ji ne, Masani
(5) A'a, cewa dai suka yi: "Ai (shi Alkur'ani) tarkacen mafarki ne, a'a, shi (Muhammadu) ƙago shi ya yi, a'a, shi mawaƙi dai ne, to sai ya zo mana da wata aya kamar yadda aka aiko wa mutanen farko."
(6) Ai babu wata al'umma da ta yi imani a gabaninsu wadda Muka hallaka; shin yanzu su za su yi imani?
(7) Kuma ba Mu aiko (wasu manzanni) gabaninka ba sai mazaje da Muke yi musu wahayi; to ku tambayi ma'abota sani idan ya zamana ku ba ku sani ba
(8) Kuma ba Mu sanya su jiki ne da ba sa cin abinci ba, kuma ba su zamanto masu dawwama ba
(9) Sannan Muka cika musu alƙawari, sai Muka tserar da su da waɗanda Muke ga damar (tserarwa) kuma Muka hallakar da maɓarnata
(10) Haƙiƙa Mun saukar muku da littafi (wanda) a cikinsa akwai ɗaukakarku[1]; me ya sa ba kwa hankalta?

(1) Watau za su samu ɗaukaka duniya da lahira idan sun yi imani da shi, suka yi aiki da karantarwarsa.

وَكَمْ قَصَمْنَا مِن قَرْيَةٍ كَانَتْ ظَالِمَةً وَأَنشَأْنَا بَعْدَهَا قَوْمًا
ءَاخَرِينَ ﴿١١﴾ فَلَمَّآ أَحَسُّوا۟ بَأْسَنَآ إِذَا هُم مِّنْهَا يَرْكُضُونَ ﴿١٢﴾
لَا تَرْكُضُوا۟ وَٱرْجِعُوٓا۟ إِلَىٰ مَآ أُتْرِفْتُمْ فِيهِ وَمَسَٰكِنِكُمْ لَعَلَّكُمْ
تُسْـَٔلُونَ ﴿١٣﴾ قَالُوا۟ يَٰوَيْلَنَآ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ﴿١٤﴾ فَمَا زَالَت تِّلْكَ
دَعْوَىٰهُمْ حَتَّىٰ جَعَلْنَٰهُمْ حَصِيدًا خَٰمِدِينَ ﴿١٥﴾ وَمَا خَلَقْنَا
ٱلسَّمَآءَ وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا لَٰعِبِينَ ﴿١٦﴾ لَوْ أَرَدْنَآ أَن نَّتَّخِذَ
لَهْوًا لَّٱتَّخَذْنَٰهُ مِن لَّدُنَّآ إِن كُنَّا فَٰعِلِينَ ﴿١٧﴾ بَلْ نَقْذِفُ بِٱلْحَقِّ
عَلَى ٱلْبَٰطِلِ فَيَدْمَغُهُۥ فَإِذَا هُوَ زَاهِقٌ ۚ وَلَكُمُ ٱلْوَيْلُ مِمَّا تَصِفُونَ
﴿١٨﴾ وَلَهُۥ مَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ وَمَنْ عِندَهُۥ لَا يَسْتَكْبِرُونَ
عَنْ عِبَادَتِهِۦ وَلَا يَسْتَحْسِرُونَ ﴿١٩﴾ يُسَبِّحُونَ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ
لَا يَفْتُرُونَ ﴿٢٠﴾ أَمِ ٱتَّخَذُوٓا۟ ءَالِهَةً مِّنَ ٱلْأَرْضِ هُمْ يُنشِرُونَ ﴿٢١﴾
لَوْ كَانَ فِيهِمَآ ءَالِهَةٌ إِلَّا ٱللَّهُ لَفَسَدَتَا ۚ فَسُبْحَٰنَ ٱللَّهِ رَبِّ ٱلْعَرْشِ
عَمَّا يَصِفُونَ ﴿٢٢﴾ لَا يُسْـَٔلُ عَمَّا يَفْعَلُ وَهُمْ يُسْـَٔلُونَ ﴿٢٣﴾ أَمِ ٱتَّخَذُوا۟
مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةً ۖ قُلْ هَاتُوا۟ بُرْهَٰنَكُمْ ۖ هَٰذَا ذِكْرُ مَن مَّعِىَ وَذِكْرُ
مَن قَبْلِى ۗ بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ٱلْحَقَّ فَهُم مُّعْرِضُونَ ﴿٢٤﴾

(11) Al'ummu nawa ne kuma Muka hallakar (waɗanda) suka kasance azzalumai, Muka kuma halicci wasu mutanen daban bayansu?
(12) Lokacin da suka fara jin azabarmu sai ga su suna guje mata
(13) (Aka ce da su): "Kada ku gudu, ku dawo zuwa ga abin da aka ni'imta ku da shi, da kuma gidajenku don a yi muku tambayoyi[1]."
(14) Suka ce: "Kaiconmu, lallai mu kam mun kasan ce azzalumai!"

(15) Sannan waccan (maganar tasu) ba su daina faɗar ta ba har Muka mai da su girbabbu, matattu (16) Kuma ba Mu halicci sama da ƙasa da kuma abin da yake tsakaninsu don wasa ba(17) In da Mun yi nufin Mu riƙi (abin) da zai shagaltar (mata ko ɗa), to da sai Mu riƙe shi daga waɗanda suke a wurinmu, idan har za Mu yi hakan
(18) A'a, ba haka ba ne, Muna jefa gaskiya a kan ƙarya, sai ta yi rugu-rugu da ita, sai (ka gan ta) ta ɓace ɓat. Kuma tsananin azaba ya tabbata a gare ku saboda abin da kuke siffanta (Shi da shi)[2]
(19) Duk kuwa waɗanda suke sammai da ƙasa nasa ne, kuma waɗanda suke wurinsa ba sa girman kai game da bauta masa, kuma ba sa gajiya
(20) Suna tasbihi dare da rana ba sa ƙosawa (21) Shin ko sun riƙi wasu ababen bauta a nan ƙasa ne waɗanda suke raya matattu? (22) Da ya zamana akwai wasu ababen bauta ba Allah ba a cikinsu (wato sammai da ƙasa), to da sun lalace. Sai dai tsarki ya tabbata ga Allah Ubangijin Al'arshi game da abin da suke siffata (Shi da shi) (23) Ba a tambayar Sa game da abin da yake aikatawa, su dai ne za a tambaye su (24) Ko kuma sun riƙi wasu ababen bauta ne ba Shi ba? Ka ce (da su): "To ku kawo dalilinku (a kan haka). Ga wa'azin waɗanda suke tare dani (watau Alƙur'ani), ga kuma wa'azin waɗanda suka gabace ni (watau littattafan annabawa sai ku duba)." A'a, yawancinsu dai ba sa sanin gaskiya sannan kuma masu bijire (mata) ne

(1) Watau a kan rayuwarsu ta tamore da bushasha. Ana faɗa musu haka a cikin izgili da tsokana.

(2) Watau na cewa yana da mata ko ɗa ko abokin tarayya.

وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيۡهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ
إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدُونِ ٢٥ وَقَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱلرَّحۡمَٰنُ وَلَدٗاۗ سُبۡحَٰنَهُۥۚ
بَلۡ عِبَادٞ مُّكۡرَمُونَ ٢٦ لَا يَسۡبِقُونَهُۥ بِٱلۡقَوۡلِ وَهُم
بِأَمۡرِهِۦ يَعۡمَلُونَ ٢٧ يَعۡلَمُ مَا بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَمَا خَلۡفَهُمۡ
وَلَا يَشۡفَعُونَ إِلَّا لِمَنِ ٱرۡتَضَىٰ وَهُم مِّنۡ خَشۡيَتِهِۦ مُشۡفِقُونَ
٢٨ ۞ وَمَن يَقُلۡ مِنۡهُمۡ إِنِّيٓ إِلَٰهٞ مِّن دُونِهِۦ فَذَٰلِكَ نَجۡزِيهِ
جَهَنَّمَۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلظَّٰلِمِينَ ٢٩ أَوَلَمۡ يَرَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ
أَنَّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ كَانَتَا رَتۡقٗا فَفَتَقۡنَٰهُمَاۖ وَجَعَلۡنَا
مِنَ ٱلۡمَآءِ كُلَّ شَيۡءٍ حَيٍّۖ أَفَلَا يُؤۡمِنُونَ ٣٠ وَجَعَلۡنَا فِي ٱلۡأَرۡضِ
رَوَٰسِيَ أَن تَمِيدَ بِهِمۡ وَجَعَلۡنَا فِيهَا فِجَاجٗا سُبُلٗا لَّعَلَّهُمۡ
يَهۡتَدُونَ ٣١ وَجَعَلۡنَا ٱلسَّمَآءَ سَقۡفٗا مَّحۡفُوظٗاۖ وَهُمۡ عَنۡ
ءَايَٰتِهَا مُعۡرِضُونَ ٣٢ وَهُوَ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ وَٱلشَّمۡسَ
وَٱلۡقَمَرَۖ كُلّٞ فِي فَلَكٖ يَسۡبَحُونَ ٣٣ وَمَا جَعَلۡنَا لِبَشَرٖ مِّن قَبۡلِكَ
ٱلۡخُلۡدَۖ أَفَإِي۟ن مِّتَّ فَهُمُ ٱلۡخَٰلِدُونَ ٣٤ كُلُّ نَفۡسٖ ذَآئِقَةُ
ٱلۡمَوۡتِۗ وَنَبۡلُوكُم بِٱلشَّرِّ وَٱلۡخَيۡرِ فِتۡنَةٗۖ وَإِلَيۡنَا تُرۡجَعُونَ ٣٥

(25) Kuma ba wani manzo da Muka aiko gabaninka face sai Mun yi masa wahayi cewa, babu wani abin bauta da gaskiya sai Ni; to sai ku bauta min(1)

(26) Suka kuma ce wai Allah Ya riƙi ɗa (daga cikin mala'iku)! Tsarki ya tabbata a gare Shi. A'a, su bayi dai ne ababen girmamawa

(27) Ba sa rigayar Sa da magana, su kuma da umarninsa suke aiki

(28) Yana sane da ayyukansu da suka gabatar da na nan gaba, ba kuma za su yi ceto ba sai ga wanda Ya yarda (daga bayinsa), suna kuwa masu kaffa-kaffa don tsoron Sa

(29) Daga cikinsu kuwa duk wanda ya ce: "Ni abin bauta ne ba shi (Allah) ba," to wannan za Mu saka masa da (wutar) Jahannama. Kamar haka kuwa Muke saka wa azzalumai

(30) Yanzu waɗanda suka kafirta ba sa ganin cewa a da can sammai da ƙasa a haɗe suke, sannan Muka raba su(2); Muka kuma halicci duk wani abu mai rai daga ruwa? To me ya sa ba za su yi imani ba?

(31) Muka kuma sanya kafaffun duwatsu a ƙasa don kar ta yi tangal-tangal da su, Muka kuma sanya wuraren tafiya a cikinta (su zama) hanyoyi don su gane (inda za su)

(32) Muka kuma sanya sama (ta zama) rufi tsararre; su kuwa (duk da haka) masu bijire wa ayoyinta (watau sama) ne

(33) Shi ne kuma Wanda Ya halicci dare da rana, da kuma rana da wata; kowannensu yana ninƙaya cikin falakinsa

(34) Ba Mu kuma sanya wa wani mutum dawwama ba a gabaninka; to yanzu idan ka mutu su ɗin masu dawwama ne?

(35) Kowanne rai zai ɗanɗani mutuwa. Muna kuwa jarrabar ku da fitinar sharri da ta alheri, kuma gare Mu ne za a dawo da ku

(1) Duk manzannin da Allah ya aiko sun zo ne da saƙon a bauta wa Allah shi kaɗai ba tare da shirka ba.

(2) Watau Allah ( ) ya fara halittar sammai da ƙasa a manne da juna daga bisani ya raba tsakaninsu.

وَإِذَا رَءَاكَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ إِن يَتَّخِذُونَكَ إِلَّا هُزُوًا أَهَٰذَا
ٱلَّذِى يَذْكُرُ ءَالِهَتَكُمْ وَهُم بِذِكْرِ ٱلرَّحْمَٰنِ هُمْ
كَٰفِرُونَ ﴿٣٦﴾ خُلِقَ ٱلْإِنسَٰنُ مِنْ عَجَلٍ ۚ سَأُو۟رِيكُمْ
ءَايَٰتِى فَلَا تَسْتَعْجِلُونِ ﴿٣٧﴾ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلْوَعْدُ
إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٣٨﴾ لَوْ يَعْلَمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ حِينَ
لَا يَكُفُّونَ عَن وُجُوهِهِمُ ٱلنَّارَ وَلَا عَن ظُهُورِهِمْ وَلَا
هُمْ يُنصَرُونَ ﴿٣٩﴾ بَلْ تَأْتِيهِم بَغْتَةً فَتَبْهَتُهُمْ فَلَا
يَسْتَطِيعُونَ رَدَّهَا وَلَا هُمْ يُنظَرُونَ ﴿٤٠﴾ وَلَقَدِ ٱسْتُهْزِئَ
بِرُسُلٍ مِّن قَبْلِكَ فَحَاقَ بِٱلَّذِينَ سَخِرُوا۟ مِنْهُم مَّا كَانُوا۟
بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿٤١﴾ قُلْ مَن يَكْلَؤُكُم بِٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ
مِنَ ٱلرَّحْمَٰنِ ۚ بَلْ هُمْ عَن ذِكْرِ رَبِّهِم مُّعْرِضُونَ ﴿٤٢﴾
أَمْ لَهُمْ ءَالِهَةٌ تَمْنَعُهُم مِّن دُونِنَا ۚ لَا يَسْتَطِيعُونَ نَصْرَ
أَنفُسِهِمْ وَلَا هُم مِّنَّا يُصْحَبُونَ ﴿٤٣﴾ بَلْ مَتَّعْنَا هَٰٓؤُلَآءِ
وَءَابَآءَهُمْ حَتَّىٰ طَالَ عَلَيْهِمُ ٱلْعُمُرُ ۗ أَفَلَا يَرَوْنَ أَنَّا نَأْتِى
ٱلْأَرْضَ نَنقُصُهَا مِنْ أَطْرَافِهَا ۚ أَفَهُمُ ٱلْغَٰلِبُونَ ﴿٤٤﴾

(36) Idan kuma waɗanda suka kafirta su ka gan ka, ba abin da suke yi maka sai izgili (suna cewa): “Yanzu wannan shi ne wanda yake aibata allolinku?” Alhali kuwa su suna kafirce wa ambaton (Allah) Mai rahama
(37) An halicci mutum da son gaggawa. Ba da daɗewa ba zan nuna muku ayoyina, to don haka kada ku nemi gaggauto da (zuwansu)
(38) Suna kuma cewa: “Wai yaushe ne wannan alƙawarin (na alƙiyama zai zo) idan kun kasance masu gaskiya?”
(39) Da waɗanda suka kafirta za su san lokacin da za su kasa kare fuskokinsu daga wuta, da kuma bayansu, ba kuma za a taimake su ba (to da ba su faɗi haka ba)
(40) A’a, za ta zo musu ne ta farat- ɗaya sai ta rikirkita su, ba kuwa za su iya kawar da ita ba, kuma su ba za a saurara musu ba
(41) Haƙiƙa kuma an yi izgili ga manzannin da suka gabace ka, sai sakamakon abin da suke yin izgili da shi ya aukar wa masu yin izgilin
(42) Ka ce (da su): “Wane ne yake kare ku dare da rana daga (azabar Allah) Mai rahama?” A’a su dai masu bijire wa ambaton Ubangijinsu ne
(43) Ko kuwa suna da ababen bauta ne da za su kare su (daga azaba) ba Mu ba? Ba za su iya taimakon kansu ba, kuma ba za a kiyaye su (daga azabarmu) ba
(44) A’a, Mun dai jiyar da waɗannan dadi ne su da iyayensu, har dai rayuwa ta tsawaita a gare su. Yanzu ba sa ganin cewa Mu Muna zo wa ƙasa Muna cinye iyakokinta da kaɗan-kaɗan[1]? Yanzu su ne masu yin rinjaye?

(1) Watau mutanen cikinta suna ta raguwa saboda mutuwa. Ko kuma Musulmi suna ƙara cinye su da yaƙi.

قُلْ إِنَّمَآ أُنذِرُكُم بِٱلْوَحْىِ ۚ وَلَا يَسْمَعُ ٱلصُّمُّ ٱلدُّعَآءَ إِذَا
مَا يُنذَرُونَ ﴿٤٥﴾ وَلَئِن مَّسَّتْهُمْ نَفْحَةٌ مِّنْ عَذَابِ رَبِّكَ
لَيَقُولُنَّ يَٰوَيْلَنَآ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ﴿٤٦﴾ وَنَضَعُ ٱلْمَوَٰزِينَ
ٱلْقِسْطَ لِيَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ فَلَا تُظْلَمُ نَفْسٌ شَيْـًٔا ۖ وَإِن كَانَ
مِثْقَالَ حَبَّةٍ مِّنْ خَرْدَلٍ أَتَيْنَا بِهَا ۗ وَكَفَىٰ بِنَا حَٰسِبِينَ ﴿٤٧﴾
وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ٱلْفُرْقَانَ وَضِيَآءً وَذِكْرًا
لِّلْمُتَّقِينَ ﴿٤٨﴾ ٱلَّذِينَ يَخْشَوْنَ رَبَّهُم بِٱلْغَيْبِ وَهُم مِّنَ ٱلسَّاعَةِ
مُشْفِقُونَ ﴿٤٩﴾ وَهَٰذَا ذِكْرٌ مُّبَارَكٌ أَنزَلْنَٰهُ ۚ أَفَأَنتُمْ لَهُۥ
مُنكِرُونَ ﴿٥٠﴾ ۞ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَآ إِبْرَٰهِيمَ رُشْدَهُۥ مِن قَبْلُ وَكُنَّا
بِهِۦ عَٰلِمِينَ ﴿٥١﴾ إِذْ قَالَ لِأَبِيهِ وَقَوْمِهِۦ مَا هَٰذِهِ ٱلتَّمَاثِيلُ ٱلَّتِىٓ
أَنتُمْ لَهَا عَٰكِفُونَ ﴿٥٢﴾ قَالُوا۟ وَجَدْنَآ ءَابَآءَنَا لَهَا عَٰبِدِينَ ﴿٥٣﴾ قَالَ
لَقَدْ كُنتُمْ أَنتُمْ وَءَابَآؤُكُمْ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٥٤﴾ قَالُوٓا۟ أَجِئْتَنَا
بِٱلْحَقِّ أَمْ أَنتَ مِنَ ٱللَّٰعِبِينَ ﴿٥٥﴾ قَالَ بَل رَّبُّكُمْ رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ ٱلَّذِى فَطَرَهُنَّ وَأَنَا۠ عَلَىٰ ذَٰلِكُم مِّنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ﴿٥٦﴾
وَتَٱللَّهِ لَأَكِيدَنَّ أَصْنَٰمَكُم بَعْدَ أَن تُوَلُّوا۟ مُدْبِرِينَ ﴿٥٧﴾

(45) Ka ce (da su): “Ni kawai ina yi muku gargaɗi ne da wahayi.” Kurame kuwa ba za su ji kira ba idan ma ana gargaɗin su
(46) Wallahi da wani ɗan furji na azabar Ubangijinka ya shafe su da tabbas za su ce: “Kaiconmu, lalle mu mun tabbata azzalumai.”
(47) Za Mu kuma sanya ma’aunai na adalci a ranar alƙiyama, sannan ba za a zalunci kowanne rai da komai ba, ko da ya zama gwargwadon ƙwayar komayya ne, za Mu zo da shi. Kuma Mun isa Masu

Musa da Haruna (Attaura) mai rarrabewa (tsakanin ƙarya da gaskiya) da kuma haske da shiriya ga masu taƙawa
(49) (Su ne) waɗanda suke tsoron Ubangijinsu ba tare da sun gan Shi ba, kuma su suna masu fargaba game da tashin alƙiyama
(50) Wannan (Alƙur’ani) kuwa tunatarwa ne mai albarka da Muka saukar da shi. Shin ku yanzu kwa riƙa musun sa?
(51) Haƙiƙa kuma Mun bai wa Ibrahimu shiriyarsa tun da farko, Mun kuma zamanto Muna sane da shi
(52) (Ka tuna) lokacin da ya ce da babansa da kuma jama’arsa: “Mene ne (amfanin) waɗannan gumakan da kuka duƙufa a bautar su?”
(53) Suka ce: “Mun sami iyayenmu suna bauta musu ne.”
(54) (Ibrahimu) ya ce: “Haƙiƙa ku da iyayen naku kun tabbata a kan ɓata bayyananne.”
(55) Suka ce: “Yanzu ka zo mana da gaskiya ne ko kuwa kai ma kana cikin masu wasa (da mu) ne?”
(56) (Ibrahimu) ya ce: “A’a, Ubangijinku dai (Shi ne) Ubangijin sammai da ƙasa, Wanda Ya halicce su, kuma ni ina daga masu shaida a kan wannan
(57) “Na rantse da Allah tabbas zan shirya wa gumakanku kaidi bayan kun tafi kun ba da baya!

فَجَعَلَهُمْ جُذَٰذًا إِلَّا كَبِيرًا لَّهُمْ لَعَلَّهُمْ إِلَيْهِ يَرْجِعُونَ
﴿٥٨﴾ قَالُوا۟ مَن فَعَلَ هَٰذَا بِـَٔالِهَتِنَآ إِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٥٩﴾
قَالُوا۟ سَمِعْنَا فَتًى يَذْكُرُهُمْ يُقَالُ لَهُۥٓ إِبْرَٰهِيمُ ﴿٦٠﴾ قَالُوا۟ فَأْتُوا۟
بِهِۦ عَلَىٰٓ أَعْيُنِ ٱلنَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَشْهَدُونَ ﴿٦١﴾ قَالُوٓا۟ ءَأَنتَ
فَعَلْتَ هَٰذَا بِـَٔالِهَتِنَا يَٰٓإِبْرَٰهِيمُ ﴿٦٢﴾ قَالَ بَلْ فَعَلَهُۥ كَبِيرُهُمْ
هَٰذَا فَسْـَٔلُوهُمْ إِن كَانُوا۟ يَنطِقُونَ ﴿٦٣﴾ فَرَجَعُوٓا۟ إِلَىٰٓ
أَنفُسِهِمْ فَقَالُوٓا۟ إِنَّكُمْ أَنتُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٦٤﴾ ثُمَّ نُكِسُوا۟
عَلَىٰ رُءُوسِهِمْ لَقَدْ عَلِمْتَ مَا هَٰٓؤُلَآءِ يَنطِقُونَ ﴿٦٥﴾ قَالَ
أَفَتَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَنفَعُكُمْ شَيْـًٔا وَلَا
يَضُرُّكُمْ ﴿٦٦﴾ أُفٍّ لَّكُمْ وَلِمَا تَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ ۖ
أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿٦٧﴾ قَالُوا۟ حَرِّقُوهُ وَٱنصُرُوٓا۟ ءَالِهَتَكُمْ إِن كُنتُمْ
فَٰعِلِينَ ﴿٦٨﴾ قُلْنَا يَٰنَارُ كُونِى بَرْدًا وَسَلَٰمًا عَلَىٰٓ إِبْرَٰهِيمَ
﴿٦٩﴾ وَأَرَادُوا۟ بِهِۦ كَيْدًا فَجَعَلْنَٰهُمُ ٱلْأَخْسَرِينَ ﴿٧٠﴾ وَنَجَّيْنَٰهُ
وَلُوطًا إِلَى ٱلْأَرْضِ ٱلَّتِى بَٰرَكْنَا فِيهَا لِلْعَٰلَمِينَ ﴿٧١﴾ وَوَهَبْنَا
لَهُۥٓ إِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ نَافِلَةً ۖ وَكُلًّا جَعَلْنَا صَٰلِحِينَ ﴿٧٢﴾

(58) Sai ya mayar da su guntu-guntu in ban da babbansu (da ya bari) don ko sa dawo masa (su tambaye shi)
(59) Suke ce: “Wane ne ya yi wa ababen bautarmu wannan (aika-aika)? Lallai shi yana daga azzalumai!”
(60) (Wasu daga cikinsu) suka ce: “Mun ji wani saurayi yana ambaton su, ana ce da shi Ibrahimu.”
(61) Suka ce: “(Ku je) ku zo da shi kan idon mutane don su shaidi (abin da ya aikata).”
(62) (Da aka kawo shi sai) suka ce: “Yanzu kai ka aikata wannan (irin aiki) ga ababen bautarmu, ya Ibrahimu?”
(63) (Ibrahimu) ya ce: “A’a, wannan babban nasu (shi) ya aikata shi, sai ku tambaye su idan ya zamana suna magana.”
(64) Sai suka koma ga (zargin) kawunansu sannan suka ce: “Lallai ku dai ne azzalumai.”
(65) Sannan aka juyo da kawunansu (zuwa kafirci) suka ce (da Ibrahimu): “Mun rantse haƙiƙa ka san cewa su waɗannan ba sa magana.”
(66) Ya ce: “To yanzu kwa riƙa bauta wa wani ba Allah ba, wanda ba zai amfana muku komai ba kuma ba zai cuce ku ba?
(67) “Tir da ku, da kuma abin da kuke bauta wa wanda ba Allah ba. To yanzu ba kwa hankalta ba?”
(68) Sai suka ce: “Ku ƙone shi ku kuma taimaki allolinku in kun kasance masu aikata hakan.”
(69) (Da suka jefa shi cikin wutar sai) Muka ce: “Ke wuta, ki zama sassanya da kuma aminci ga Ibrahimu!”
(70) Suka yi nufin shirya masa makirci sai Muka mayar da su taɓaɓɓu
(71) Muka kuma tserar da shi, shi da Luɗu zuwa ga ƙasar da Muka yi albarka a cikinta ga talikai (watau Sham)
(72) Muka kuma ba shi Is’haƙa da kuma Ya’aƙubu ƙari (wato jika). Dukkanninsu kuma Mun sanya su salihai

وَجَعَلْنَٰهُمْ أَئِمَّةً يَهْدُونَ بِأَمْرِنَا وَأَوْحَيْنَآ إِلَيْهِمْ فِعْلَ
ٱلْخَيْرَٰتِ وَإِقَامَ ٱلصَّلَوٰةِ وَإِيتَآءَ ٱلزَّكَوٰةِ ۖ وَكَانُوا۟ لَنَا
عَٰبِدِينَ ﴿٧٣﴾ وَلُوطًا ءَاتَيْنَٰهُ حُكْمًا وَعِلْمًا وَنَجَّيْنَٰهُ مِنَ
ٱلْقَرْيَةِ ٱلَّتِى كَانَت تَّعْمَلُ ٱلْخَبَٰٓئِثَ ۚ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ قَوْمَ سَوْءٍ
فَٰسِقِينَ ﴿٧٤﴾ وَأَدْخَلْنَٰهُ فِى رَحْمَتِنَآ ۖ إِنَّهُۥ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ
﴿٧٥﴾ وَنُوحًا إِذْ نَادَىٰ مِن قَبْلُ فَٱسْتَجَبْنَا لَهُۥ فَنَجَّيْنَٰهُ
وَأَهْلَهُۥ مِنَ ٱلْكَرْبِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٧٦﴾ وَنَصَرْنَٰهُ مِنَ ٱلْقَوْمِ
ٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَآ ۚ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ قَوْمَ سَوْءٍ فَأَغْرَقْنَٰهُمْ
أَجْمَعِينَ ﴿٧٧﴾ وَدَاوُۥدَ وَسُلَيْمَٰنَ إِذْ يَحْكُمَانِ فِى ٱلْحَرْثِ
إِذْ نَفَشَتْ فِيهِ غَنَمُ ٱلْقَوْمِ وَكُنَّا لِحُكْمِهِمْ شَٰهِدِينَ ﴿٧٨﴾
فَفَهَّمْنَٰهَا سُلَيْمَٰنَ ۚ وَكُلًّا ءَاتَيْنَا حُكْمًا وَعِلْمًا ۚ وَسَخَّرْنَا
مَعَ دَاوُۥدَ ٱلْجِبَالَ يُسَبِّحْنَ وَٱلطَّيْرَ ۚ وَكُنَّا فَٰعِلِينَ ﴿٧٩﴾
وَعَلَّمْنَٰهُ صَنْعَةَ لَبُوسٍ لَّكُمْ لِتُحْصِنَكُم مِّنۢ بَأْسِكُمْ ۖ
فَهَلْ أَنتُمْ شَٰكِرُونَ ﴿٨٠﴾ وَلِسُلَيْمَٰنَ ٱلرِّيحَ عَاصِفَةً تَجْرِى بِأَمْرِهِۦٓ
إِلَى ٱلْأَرْضِ ٱلَّتِى بَٰرَكْنَا فِيهَا ۚ وَكُنَّا بِكُلِّ شَىْءٍ عَٰلِمِينَ ﴿٨١﴾

(73) Muka kuma sanya su shugabanni masu shiryarwa da umarninmu, Muka kuma yi musu wahayi na aikata alheri da tsai da salla da ba da zakka, sun kuwa zamanto masu bauta mana ne

(74) Ludu kuma Muka ba shi hukunci da ilimi, Muka kuma tserar da shi daga alkaryar nan da (mutanenta) suka zamanto suna aikata munanan ayyuka. Lallai su sun kasance mutanen banza ne fasikai

(75) Muka kuma shigar da shi cikin rahamarmu; lallai shi yana daga (cikin) mutane na

(76) (Ka tuna) lokacin da Nuhu ya roki Ubangijinsa tun a da can[1], sannan Muka amsa masa (rokonsa) Muka tserar da shi da iyalinsa daga bakin ciki mai girma

(77) Muka kuma taimake shi bisa mutanen da suka karyata ayoyinmu. Lalle su sun kasance mutanen banza, sai Muka nutsar da su gaba daya

(78) (Ka tuna) kuma Dawuda da Sulaimanu lokacin da suke yin hukunci a kan amfanin gona lokacin da dabbobin wasu mutane suka cinye shi da daddare, Mun kuwa zamanto Muna sane da irin hukuncin nasu

(79) Sai Muka ganar da Sulaimanu shi (hukuncin)[2]. Kuma dukkaninsu Mun ba su annabta da ilimi. Muka kuma hore wa Dawuda duwatsu da tsuntsaye, suna tasbihi tare da shi. Mun kuwa kasance Masu aikata (haka)

(80) Muka kuma koya masa yadda ake kera silke dominku don ya kare ku lokacin yakinku; to shin ku masu godiya ne?

(81) Sulaimanu kuwa (Muka hore masa) iska mai karfi tana gudu da umarninsa zuwa kasar da Muka yi albarka a cikinta, (watau Sham). Mun kuwa kasance Masana ga kowanne abu

(1) Duba Suratu Nuh, aya ta 26-28.

(2) Da farko Annabi Dawud ( ) ya yi hukunci da cewa, manomin zai karbi dabbobin a madadin amfanin gonarsa da suka cinye. Amma sai Sulaiman ( ) ya sake hukunci da cewa, manomin zai rike dabbobin yana amfanuwa da su har zuwa lokacin da masu dabbobin za su sake noma musu gonarsa ta dawo kamar farko sai su karbi dabbobinsu.

وَمِنَ ٱلشَّيَٰطِينِ مَن يَغُوصُونَ لَهُۥ وَيَعۡمَلُونَ عَمَلٗا دُونَ
ذَٰلِكَۖ وَكُنَّا لَهُمۡ حَٰفِظِينَ ٨٢ ۞ وَأَيُّوبَ إِذۡ نَادَىٰ
رَبَّهُۥٓ أَنِّي مَسَّنِيَ ٱلضُّرُّ وَأَنتَ أَرۡحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ ٨٣
فَٱسۡتَجَبۡنَا لَهُۥ فَكَشَفۡنَا مَا بِهِۦ مِن ضُرّٖۖ وَءَاتَيۡنَٰهُ أَهۡلَهُۥ
وَمِثۡلَهُم مَّعَهُمۡ رَحۡمَةٗ مِّنۡ عِندِنَا وَذِكۡرَىٰ لِلۡعَٰبِدِينَ
٨٤ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِدۡرِيسَ وَذَا ٱلۡكِفۡلِۖ كُلّٞ مِّنَ ٱلصَّٰبِرِينَ
٨٥ وَأَدۡخَلۡنَٰهُمۡ فِي رَحۡمَتِنَآۖ إِنَّهُم مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ٨٦
وَذَا ٱلنُّونِ إِذ ذَّهَبَ مُغَٰضِبٗا فَظَنَّ أَن لَّن نَّقۡدِرَ عَلَيۡهِ
فَنَادَىٰ فِي ٱلظُّلُمَٰتِ أَن لَّآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنتَ سُبۡحَٰنَكَ إِنِّي
كُنتُ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٨٧ فَٱسۡتَجَبۡنَا لَهُۥ وَنَجَّيۡنَٰهُ
مِنَ ٱلۡغَمِّۚ وَكَذَٰلِكَ نُنجِي ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٨٨ وَزَكَرِيَّآ
إِذۡ نَادَىٰ رَبَّهُۥ رَبِّ لَا تَذَرۡنِي فَرۡدٗا وَأَنتَ خَيۡرُ ٱلۡوَٰرِثِينَ
٨٩ فَٱسۡتَجَبۡنَا لَهُۥ وَوَهَبۡنَا لَهُۥ يَحۡيَىٰ وَأَصۡلَحۡنَا
لَهُۥ زَوۡجَهُۥٓۚ إِنَّهُمۡ كَانُواْ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِ
وَيَدۡعُونَنَا رَغَبٗا وَرَهَبٗاۖ وَكَانُواْ لَنَا خَٰشِعِينَ ٩٠

(82) Akwai kuma wasu aljannu da suke nutso don fito masa (da lu'u-lu'u) suna kuma yin wani aikin ban da wannan (kamar gine-gine); Mun zamanto kuma Masu kula da su))

(83) Kuma (ka tuna) Ayyuba lokacin da ya roƙi Ubangijinsa (yana cewa): "Lallai cuta ta same ni, Kai ne kuwa Mafi jin ƙan masu jin ƙai!"

(84) Sai Muka amsa masa (roƙonsa) sannan Muka yaye cutar da take tare da shi, Muka kuma ba shi (madadin) kwatankwacinsu tare da su don jin ƙai daga gare Mu da kuma wa'azi ga masu bauta (ga Allah)

(85) Na Ismail, na Idris, na Dhulkifli, wote walikuwa miongoni mwa wanao subiri

(86) Muka kuma shigar da su cikin rahamarmu; lalle su suna daga bayi na gari

(87) Kuma (ka tuna) ma'abocin kifi (wato Yunusa) lokacin da ya tafi yana cike da fushi(1), sannan ya zaci cewa ba za Mu ƙuntata masa ba, sai ya kira (Mu) a cikin duffai(2) yana cewa: "Ba wani abin bauta da gaskiya sai Kai (ya Allah), tsarki ya tabbata a gare Ka, lallai ni na kasance cikin azzalumai!"

(88) Sai Muka amsa masa Muka kuma tserar da shi daga baƙin ciki. Kamar haka kuwa Muke tserar da muminai

(89) (Ka tuna) kuma Zakariya'u lokacin da ya roƙi Ubangijinsa (cewa): "Ya Ubangijina, kada Ka bar ni ni kaɗai (ba magaji), Kai ne kuwa Fiyayyen magada."

(90) Sai Muka amsa masa Muka ba shi Yahya, Muka kuma gyara masa (mahaifar) matarsa. Lallai su sun kasance suna gaggawa wajen yin alherai, suna kuma roƙon Mu suna masu kwaɗayin (rahamarmu) masu kuma tsoron (azabarmu), sun kuma zamanto masu ƙaskantar da kai gare Mu

(1) Watau saboda mutanensa sun kafe a kan kafirci sun ƙi yin imani.

(2) Watau duhun dare da duhun kogi da duhun cikin kifi.

وَٱلَّتِيٓ أَحۡصَنَتۡ فَرۡجَهَا فَنَفَخۡنَا فِيهَا مِن رُّوحِنَا
وَجَعَلۡنَٰهَا وَٱبۡنَهَآ ءَايَةٗ لِّلۡعَٰلَمِينَ ﴿٩١﴾ إِنَّ هَٰذِهِۦٓ
أُمَّتُكُمۡ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ وَأَنَا۠ رَبُّكُمۡ فَٱعۡبُدُونِ ﴿٩٢﴾
وَتَقَطَّعُوٓاْ أَمۡرَهُم بَيۡنَهُمۡۖ كُلٌّ إِلَيۡنَا رَٰجِعُونَ ﴿٩٣﴾
فَمَن يَعۡمَلۡ مِنَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَلَا كُفۡرَانَ
لِسَعۡيِهِۦ وَإِنَّا لَهُۥ كَٰتِبُونَ ﴿٩٤﴾ وَحَرَٰمٌ عَلَىٰ قَرۡيَةٍ
أَهۡلَكۡنَٰهَآ أَنَّهُمۡ لَا يَرۡجِعُونَ ﴿٩٥﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا فُتِحَتۡ
يَأۡجُوجُ وَمَأۡجُوجُ وَهُم مِّن كُلِّ حَدَبٖ يَنسِلُونَ ﴿٩٦﴾
وَٱقۡتَرَبَ ٱلۡوَعۡدُ ٱلۡحَقُّ فَإِذَا هِيَ شَٰخِصَةٌ أَبۡصَٰرُ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ يَٰوَيۡلَنَا قَدۡ كُنَّا فِي غَفۡلَةٖ مِّنۡ هَٰذَا بَلۡ كُنَّا
ظَٰلِمِينَ ﴿٩٧﴾ إِنَّكُمۡ وَمَا تَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
حَصَبُ جَهَنَّمَ أَنتُمۡ لَهَا وَٰرِدُونَ ﴿٩٨﴾ لَوۡ كَانَ
هَٰٓؤُلَآءِ ءَالِهَةٗ مَّا وَرَدُوهَاۖ وَكُلّٞ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿٩٩﴾
لَهُمۡ فِيهَا زَفِيرٞ وَهُمۡ فِيهَا لَا يَسۡمَعُونَ ﴿١٠٠﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ
سَبَقَتۡ لَهُم مِّنَّا ٱلۡحُسۡنَىٰٓ أُوْلَٰٓئِكَ عَنۡهَا مُبۡعَدُونَ ﴿١٠١﴾

(91) (Ka tuna) kuma wadda ta tsare matancinta, sai Muka yi busa a cikinta daga Ruhinmu, Muka kuma sanya ta ita da ɗanta aya ga talikai
(92) Lallai wannan addini naku guda ɗaya ne (wato Musulunci), kuma Ni ne Ubangijinku, to ku bauta min
(93) Sannan sai suka rarraba al'amarinsu (na addini) a tsakaninsu; dukkaninsu dai masu komowa ne zuwa gare Mu
(94) To duk wanda ya aikata kyawawan ayyuka alhali kuwa shi mumini ne, to babu musantawa ga aikinsa(1), lallai kuma Mu Masu rubuta masa shi ne
(95) Kuma haramun ne ga (duk) wata al'umma da Muka hallaka cewa za su komo (duniya)(96) Har sai lokacin da aka buɗe Yajuju da Majuju, su kuwa za su gangaro ne ta kowanne tudu
(97) Kuma alƙawarin gaskiya ya gabato, sai ga shi idanuwan waɗanda suka kafirta sun yi zuru-zuru (suna cewa): "Kaiconmu! Haƙiƙa mun kasance cikin gafala game da wannan (ranar); a'a, kai mu dai mun kasance azzalumai ne!"
(98) (Sai a ce da su): "Lallai ku da abin da kuke bauta wa ba Allah ba, (duka) makamashin Jahannama ne, kuma ku masu shigar ta ne."
(99) Da waɗancan (gumakan) sun kasance alloli (na gaske) da ba su shiga cikinta ba, dukkaninsu kuwa madawwama ne a cikinta
(100) Suna ta ƙaraji a cikinta, alhali kuwa su a cikinta ba sa jin (sautin komai)
(101) Lalle waɗanda kalmarmu mafi kyau (ta cewa su 'yan Aljanna ne) ta riga ta tabbata gare su, waɗannan waɗanda ake nesantawa ne daga gare ta (wutar)

(1) Watau ba za a yi masa runton aikinsa mai kyau ba, za a yi masa kyakkyawar sakayya ne a kai.

لَا يَسْمَعُونَ حَسِيسَهَا ۖ وَهُمْ فِي مَا اشْتَهَتْ أَنفُسُهُمْ
خَالِدُونَ ﴿١٠٢﴾ لَا يَحْزُنُهُمُ الْفَزَعُ الْأَكْبَرُ وَتَتَلَقَّاهُمُ
الْمَلَائِكَةُ هَٰذَا يَوْمُكُمُ الَّذِي كُنتُمْ تُوعَدُونَ ﴿١٠٣﴾
يَوْمَ نَطْوِي السَّمَاءَ كَطَيِّ السِّجِلِّ لِلْكُتُبِ ۚ كَمَا بَدَأْنَا
أَوَّلَ خَلْقٍ نُّعِيدُهُ ۚ وَعْدًا عَلَيْنَا ۚ إِنَّا كُنَّا فَاعِلِينَ ﴿١٠٤﴾ وَلَقَدْ
كَتَبْنَا فِي الزَّبُورِ مِن بَعْدِ الذِّكْرِ أَنَّ الْأَرْضَ يَرِثُهَا
عِبَادِيَ الصَّالِحُونَ ﴿١٠٥﴾ إِنَّ فِي هَٰذَا لَبَلَاغًا لِّقَوْمٍ
عَابِدِينَ ﴿١٠٦﴾ وَمَا أَرْسَلْنَاكَ إِلَّا رَحْمَةً لِّلْعَالَمِينَ
﴿١٠٧﴾ قُلْ إِنَّمَا يُوحَىٰ إِلَيَّ أَنَّمَا إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَاحِدٌ ۖ فَهَلْ
أَنتُم مُّسْلِمُونَ ﴿١٠٨﴾ فَإِن تَوَلَّوْا فَقُلْ آذَنتُكُمْ عَلَىٰ سَوَاءٍ ۖ
وَإِنْ أَدْرِي أَقَرِيبٌ أَم بَعِيدٌ مَّا تُوعَدُونَ ﴿١٠٩﴾ إِنَّهُ يَعْلَمُ
الْجَهْرَ مِنَ الْقَوْلِ وَيَعْلَمُ مَا تَكْتُمُونَ ﴿١١٠﴾ وَإِنْ أَدْرِي
لَعَلَّهُ فِتْنَةٌ لَّكُمْ وَمَتَاعٌ إِلَىٰ حِينٍ ﴿١١١﴾ قَالَ رَبِّ احْكُم
بِالْحَقِّ ۗ وَرَبُّنَا الرَّحْمَٰنُ الْمُسْتَعَانُ عَلَىٰ مَا تَصِفُونَ ﴿١١٢﴾

سُورَةُ الْحَجِّ

(102) Ba za su ji hargowarta ba, kuma su masu dawwama ne cikin abin da ransu yake so
(103) Babbar firgitar (wannan ranar) ba ta samun su, kuma mala'iku za su tare su, (suna cewa): "Wannan ita ce ranar taku wadda kuka zamanto ana yi muku alƙawarinta (a duniya)."
(104) (Ita ce) ranar da za Mu naɗe sama kamar naɗin marubuci ga takardu. Kamar yadda Muka ƙagi halitta da farko (haka) za Mu mai da ita. Wannan alƙawari ne da Muka ɗauka. Lallai Mun kasance Masu aikata (haka)
(105) Kuma haƙiƙa Mun rubuta cikin saukakkun littattafai bayan (an rubuta a Lauhul-Mahfuzu) cewa, ita ƙasa bayina na gari ne za su gaje ta
(106) Lallai a cikin wannan (Alƙur'ani) akwai isar da saƙo ga mutane masu bauta
(107) Ba Mu aiko ka ba sai don rahama ga talikai
(108) Ka ce (da su): "Abin da kawai ake yiwo min wahayinsa (shi ne) lallai abin bautar ku Allah ne Guda Ɗaya; to shin ko za ku miƙa wuya?"
(109) To idan sun ba da baya sai ka ce (da su): "Na sanar da ku cewa ni da ku muna kan abu ɗaya ne (wato ta-ware). Kuma ni ban sani ba, shin abin da ake yi muku alƙawari da shi(1) kusa yake ko kuwa nesa?
(110) "Lalle Shi (Allah) Yana sane da (abin da kuke) bayyanawa na magana Yana kuma sane da abin da kuke ɓoyewa
(111) "Kuma ban sani ba ko watakila shi (jinkirta azabtar da ku) fitina ne a gare ku da kuma jin daɗi zuwa wani ɗan lokaci
(112) (Annabi Muhammadu) ya ce: "Ya Ubangijina, Ka yi hukunci (tsakanina da kafirai) da gaskiya. Ubangijinmu kuwa (Shi ne) Ar-Rahamanu Wanda ake neman taimakonsa a kan abin da kuke siffantawa."

(1) Watau alƙawarin zuwan azabar Allah a gare su.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱتَّقُواْ رَبَّكُمْۚ إِنَّ زَلْزَلَةَ ٱلسَّاعَةِ شَيْءٌ عَظِيمٌ
١ يَوْمَ تَرَوْنَهَا تَذْهَلُ كُلُّ مُرْضِعَةٍ عَمَّآ أَرْضَعَتْ وَتَضَعُ
كُلُّ ذَاتِ حَمْلٍ حَمْلَهَا وَتَرَى ٱلنَّاسَ سُكَٰرَىٰ وَمَا هُم
بِسُكَٰرَىٰ وَلَٰكِنَّ عَذَابَ ٱللَّهِ شَدِيدٌ ٢ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن
يُجَٰدِلُ فِي ٱللَّهِ بِغَيْرِ عِلْمٍ وَيَتَّبِعُ كُلَّ شَيْطَٰنٍ مَّرِيدٍ ٣
كُتِبَ عَلَيْهِ أَنَّهُۥ مَن تَوَلَّاهُ فَأَنَّهُۥ يُضِلُّهُۥ وَيَهْدِيهِ
إِلَىٰ عَذَابِ ٱلسَّعِيرِ ٤ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِن كُنتُمْ فِي رَيْبٍ
مِّنَ ٱلْبَعْثِ فَإِنَّا خَلَقْنَٰكُم مِّن تُرَابٍ ثُمَّ مِن نُّطْفَةٍ
ثُمَّ مِنْ عَلَقَةٍ ثُمَّ مِن مُّضْغَةٍ مُّخَلَّقَةٍ وَغَيْرِ مُخَلَّقَةٍ لِّنُبَيِّنَ
لَكُمْۚ وَنُقِرُّ فِي ٱلْأَرْحَامِ مَا نَشَآءُ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى ثُمَّ
نُخْرِجُكُمْ طِفْلًا ثُمَّ لِتَبْلُغُوٓاْ أَشُدَّكُمْۖ وَمِنكُم مَّن يُتَوَفَّىٰ
وَمِنكُم مَّن يُرَدُّ إِلَىٰٓ أَرْذَلِ ٱلْعُمُرِ لِكَيْلَا يَعْلَمَ مِنۢ
بَعْدِ عِلْمٍ شَيْـًٔاۚ وَتَرَى ٱلْأَرْضَ هَامِدَةً فَإِذَآ أَنزَلْنَا عَلَيْهَا
ٱلْمَآءَ ٱهْتَزَّتْ وَرَبَتْ وَأَنۢبَتَتْ مِن كُلِّ زَوْجٍۭ بَهِيجٍ ٥

Sura Hajji

(1) Ya ku mutane, ku kiyaye dokokin Ubangijinku. Lalle girgizar (ranar) alƙiyama abu ne mai girma
(2) Ranar da za ku gan ta, (don tsananin firgita) kowacce mai shayarwa za ta manta da abin da ta shayar, kuma kowacce mai ciki ta zubar da cikinta, ka ga kuma mutane suna tangaɗi, alhali kuwa ba bugaggu ba ne, sai dai azabar Allah ce mai tsanani
(3) Daga mutane kuma wanda yake jayayya game da Allah ba tare da wani ilimi ba, kuma yake bin kowanne shaiɗani mai tsaurin kai
(4) An ƙaddara masa (wato Shaiɗan) cewa duk wanda ya rungume shi to haƙiƙa zai ɓatar da shi kuma ya ja shi zuwa ga azaba ta (wutar) Sa'ira
(5) Ya ku mutane, idan kun zamanto cikin kokwanton tashi (bayan mutuwa), to lalle Mu Muka halicce ku daga ƙasa, sannan daga maniyyi, sannan daga gudan jini, sannan daga tsoka, mai cikakkiyar halitta da kuma wadda ba cikakkiya ba(1), don Mu bayyana muku (Ikonmu). Kuma Muna tabbatar da abin da Muka ga dama a cikin mahaifa har zuwa wani lokaci ƙayyadajje, sannan kuma Mu fito da ku kuna jarirai, sannan kuma don ku kai cikar ƙarfinku; daga cikinku akwai wanda za a karɓi ransa, akwai kuma wanda za a bari har zuwa mafi ƙasƙantar rayuwa don ya kai ga halin da ba zai san komai ba bayan kuwa da can ya sani. Za ka kuma ga ƙasa a ƙeƙashe, sannan idan Muka saukar mata da ruwa sai ta girgiza ta kumbura kuma ta fitar da kowanne irin tsiro mai ƙayatarwa

(1) Watau tsokar ta zama wata halitta wadda ba cikakken mutum ba, daga bisani a yi ɓarin ta.

ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْحَقُّ وَأَنَّهُۥ يُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰ وَأَنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ
قَدِيرٌ ﴿٦﴾ وَأَنَّ ٱلسَّاعَةَ ءَاتِيَةٌ لَّا رَيْبَ فِيهَا وَأَنَّ ٱللَّهَ يَبْعَثُ مَن فِى
ٱلْقُبُورِ ﴿٧﴾ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يُجَٰدِلُ فِى ٱللَّهِ بِغَيْرِ عِلْمٍ وَلَا هُدًى
وَلَا كِتَٰبٍ مُّنِيرٍ ﴿٨﴾ ثَانِىَ عِطْفِهِۦ لِيُضِلَّ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ ۖ لَهُۥ فِى
ٱلدُّنْيَا خِزْىٌ ۖ وَنُذِيقُهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ عَذَابَ ٱلْحَرِيقِ ﴿٩﴾ ذَٰلِكَ
بِمَا قَدَّمَتْ يَدَاكَ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَيْسَ بِظَلَّٰمٍ لِّلْعَبِيدِ ﴿١٠﴾ وَمِنَ ٱلنَّاسِ
مَن يَعْبُدُ ٱللَّهَ عَلَىٰ حَرْفٍ ۖ فَإِنْ أَصَابَهُۥ خَيْرٌ ٱطْمَأَنَّ بِهِۦ ۖ وَإِنْ
أَصَابَتْهُ فِتْنَةٌ ٱنقَلَبَ عَلَىٰ وَجْهِهِۦ خَسِرَ ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةَ ۚ ذَٰلِكَ
هُوَ ٱلْخُسْرَانُ ٱلْمُبِينُ ﴿١١﴾ يَدْعُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَضُرُّهُۥ وَ
وَمَا لَا يَنفَعُهُۥ ۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلضَّلَٰلُ ٱلْبَعِيدُ ﴿١٢﴾ يَدْعُوا۟ لَمَن
ضَرُّهُۥٓ أَقْرَبُ مِن نَّفْعِهِۦ ۖ لَبِئْسَ ٱلْمَوْلَىٰ وَلَبِئْسَ ٱلْعَشِيرُ ﴿١٣﴾
إِنَّ ٱللَّهَ يُدْخِلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ جَنَّٰتٍ
تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَفْعَلُ مَا يُرِيدُ ﴿١٤﴾ مَن كَانَ
يَظُنُّ أَن لَّن يَنصُرَهُ ٱللَّهُ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ فَلْيَمْدُدْ بِسَبَبٍ إِلَى
ٱلسَّمَآءِ ثُمَّ لْيَقْطَعْ فَلْيَنظُرْ هَلْ يُذْهِبَنَّ كَيْدُهُۥ مَا يَغِيظُ ﴿١٥﴾



(6) Wannan (kuwa) saboda lalle Allah Shi ne gaskiya, kuma lalle Shi ne Yake raya matattu, kuma lalle Mai iko ne a kan komai

(7) Kuma lalle Alkiyama za ta zo babu kokwanto game da ita, kuma lalle Allah zai tashi waɗanda suke cikin ƙaburbura

(8) Daga mutane kuma akwai wanda yake jayayya game da (al'amarin) Allah ba tare da ilimi ba ko shiriya ko kuma wani littafi mai haske

(9) Yana juyar da kansa don ya ɓatar da (mutane) daga hanyar Allah; yana da

Mu ɗanɗana masa azabar ƙuna(10) (Za a ce da shi): "Wannan (kuwa) saboda abin da hannayenka suka aikata ne, kuma lalle Allah ba Mai zaluntar bayi ba ne."

(11) Daga mutane kuma akwai wanda yake bauta wa Allah a kan gaɓa[1]; to idan alheri ya same shi sai ya nutsu da shi, idan kuwa wata masifa ta same shi sai ya juya a kan fuskarsa; to ya yi hasarar duniya da lahira. Wannan (kuwa) ita ce hasara bayyananniya

(12) Yana bauta wa wanin Allah, abin da ba zai cuce shi ba kuma ba zai amfane shi ba. Wannan kuwa shi ne ɓata mai nisa

(13) Yana bauta wa abin da cutarsa ta fi kusa fiye da amfaninsa. Tabbas mataimaki ya munana, kuma tabbas aboki ya munana

(14) Lalle Allah Yana shigar da waɗanda suka yi imani kuma suka yi aiki na gari gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Lalle Allah Yana aikata abin da Ya ga dama

(15) Wanda ya zamanto yana tsammanin cewa Allah ba zai taimake shi ba, (wato Annabinsa) a duniya da lahira, to sai ya hau sama da igiya, sannan ya yanke ta[2], ya duba shin wannan mugun tanadi nasa zai kawar da abin da yake cike da haushinsa?

(1) Watau yana bautar Allah cikin shakku, shi ne munafuki.

(2) Watau ya faɗo ƙasa; ko kuma ya shaƙe kansa da ita.

وَكَذَٰلِكَ أَنزَلْنَٰهُ ءَايَٰتٍۭ بَيِّنَٰتٍ وَأَنَّ ٱللَّهَ يَهْدِى مَن يُرِيدُ
﴿١٦﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَٱلَّذِينَ هَادُوا۟ وَٱلصَّٰبِـُٔونَ وَٱلنَّصَٰرَىٰ
وَٱلْمَجُوسَ وَٱلَّذِينَ أَشْرَكُوٓا۟ إِنَّ ٱللَّهَ يَفْصِلُ بَيْنَهُمْ يَوْمَ
ٱلْقِيَٰمَةِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ شَهِيدٌ ﴿١٧﴾ أَلَمْ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ
يَسْجُدُ لَهُۥ مَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِى ٱلْأَرْضِ وَٱلشَّمْسُ
وَٱلْقَمَرُ وَٱلنُّجُومُ وَٱلْجِبَالُ وَٱلشَّجَرُ وَٱلدَّوَآبُّ وَكَثِيرٌ مِّنَ
ٱلنَّاسِ ۖ وَكَثِيرٌ حَقَّ عَلَيْهِ ٱلْعَذَابُ ۗ وَمَن يُهِنِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن
مُّكْرِمٍ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَفْعَلُ مَا يَشَآءُ ﴿١٨﴾ ۞ هَٰذَانِ خَصْمَانِ
ٱخْتَصَمُوا۟ فِى رَبِّهِمْ ۖ فَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ قُطِّعَتْ لَهُمْ ثِيَابٌ
مِّن نَّارٍ يُصَبُّ مِن فَوْقِ رُءُوسِهِمُ ٱلْحَمِيمُ ﴿١٩﴾ يُصْهَرُ بِهِۦ
مَا فِى بُطُونِهِمْ وَٱلْجُلُودُ ﴿٢٠﴾ وَلَهُم مَّقَٰمِعُ مِنْ حَدِيدٍ ﴿٢١﴾ كُلَّمَآ
أَرَادُوٓا۟ أَن يَخْرُجُوا۟ مِنْهَا مِنْ غَمٍّ أُعِيدُوا۟ فِيهَا وَذُوقُوا۟ عَذَابَ
ٱلْحَرِيقِ ﴿٢٢﴾ إِنَّ ٱللَّهَ يُدْخِلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ يُحَلَّوْنَ فِيهَا مِنْ
أَسَاوِرَ مِن ذَهَبٍ وَلُؤْلُؤًا ۖ وَلِبَاسُهُمْ فِيهَا حَرِيرٌ ﴿٢٣﴾

(16) Kamar haka kuwa Muka saukar da shi (Alkur'ani) ayoyi mabayyana, kuma lalle Allah Yana shiryar da wanda Yake nufin (shiryar da shi)
(17) Lalle waɗanda suka yi imani da waɗanda suka zama Yahudawa da Sabi'awa da waɗanda suka zama Majusawa da kuma waɗanda suka yi shirka, lalle Allah zai yi hukunci a tsakaninsu ranar alƙiyama. Lalle Allah Mai ganin kowane abu ne
(18) Shin ba ka san cewa duk abin da yake cikin sammai da ƙasa suna yin sujjada ne ga Allah ba, (haka ma) rana da wata da taurari da duwatsu da bishiyoyi da dabbobi da kuma mutane masu yawa; da yawa kuma azaba ta tabbata a kansu? Duk kuwa wanda Allah Ya wulaƙanta, to ba shi da wani mai girmama shi. Lalle Allah Yana aikata abin da Ya ga dama
(19) Biyu ɗin nan (muminai da kafirai) masu jayayya ne da suka yi jayayya game da Ubangijinsu (wato addininsu); waɗanda suka kafirce sai aka ɗinka musu tufafi na wuta, kuma ana zuba musu tafasasshen ruwa ta saman kawunansu
(20) Ana narka abin da yake cikinsu da shi (tafasasshen ruwan) da kuma fatu
(21) Suna kuma (shan duka) da gudumomi na baƙin ƙarfe
(22) Duk sanda suka yi nufin fita daga cikinta (wutar) saboda baƙin ciki sai a sake mayar da su cikinta, (a ce da su): "Ku ɗanɗani azabar gobara."
(23) Lalle Allah Yana shigar da waɗanda suka yi imani kuma suka yi ayyuka na gari gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, ana yi musu ado a cikinsu da awarwaro na zinare da kuma lu'ulu'u; tufafinsu kuwa a cikinsu alharini ne

وَهُدُوٓاْ إِلَى ٱلطَّيِّبِ مِنَ ٱلۡقَوۡلِ وَهُدُوٓاْ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلۡحَمِيدِ
﴿٢٤﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلۡمَسۡجِدِ
ٱلۡحَرَامِ ٱلَّذِي جَعَلۡنَٰهُ لِلنَّاسِ سَوَآءً ٱلۡعَٰكِفُ فِيهِ وَٱلۡبَادِۚ
وَمَن يُرِدۡ فِيهِ بِإِلۡحَادِۭ بِظُلۡمٖ نُّذِقۡهُ مِنۡ عَذَابٍ أَلِيمٖ
﴿٢٥﴾ وَإِذۡ بَوَّأۡنَا لِإِبۡرَٰهِيمَ مَكَانَ ٱلۡبَيۡتِ أَن لَّا تُشۡرِكۡ
بِي شَيۡـٔٗا وَطَهِّرۡ بَيۡتِيَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلۡقَآئِمِينَ وَٱلرُّكَّعِ
ٱلسُّجُودِ ﴿٢٦﴾ وَأَذِّن فِي ٱلنَّاسِ بِٱلۡحَجِّ يَأۡتُوكَ رِجَالٗا وَعَلَىٰ
كُلِّ ضَامِرٖ يَأۡتِينَ مِن كُلِّ فَجٍّ عَمِيقٖ ﴿٢٧﴾ لِّيَشۡهَدُواْ
مَنَٰفِعَ لَهُمۡ وَيَذۡكُرُواْ ٱسۡمَ ٱللَّهِ فِيٓ أَيَّامٖ مَّعۡلُومَٰتٍ
عَلَىٰ مَا رَزَقَهُم مِّنۢ بَهِيمَةِ ٱلۡأَنۡعَٰمِۖ فَكُلُواْ مِنۡهَا
وَأَطۡعِمُواْ ٱلۡبَآئِسَ ٱلۡفَقِيرَ ﴿٢٨﴾ ثُمَّ لۡيَقۡضُواْ تَفَثَهُمۡ
وَلۡيُوفُواْ نُذُورَهُمۡ وَلۡيَطَّوَّفُواْ بِٱلۡبَيۡتِ ٱلۡعَتِيقِ ﴿٢٩﴾
ذَٰلِكَۖ وَمَن يُعَظِّمۡ حُرُمَٰتِ ٱللَّهِ فَهُوَ خَيۡرٞ لَّهُۥ عِندَ
رَبِّهِۦۗ وَأُحِلَّتۡ لَكُمُ ٱلۡأَنۡعَٰمُ إِلَّا مَا يُتۡلَىٰ عَلَيۡكُمۡۖ
فَٱجۡتَنِبُواْ ٱلرِّجۡسَ مِنَ ٱلۡأَوۡثَٰنِ وَٱجۡتَنِبُواْ قَوۡلَ ٱلزُّورِ ﴿٣٠﴾

(24) Kuma an shiryar da su zuwa ga magana mai dadi (a duniya, wato Kalmar Shahada), an kuma shiryar da su zuwa ga tafarkin (Allah) Sha-yabo

(25) Lalle wadanda suka kafirta suke kuma toshe hanyar Allah da kuma Masallacin Harami wanda Muka sanya shi bai-daya ga mutane, mazaunin cikinsa da kuma mai zuwa (daga waje). Wanda kuwa ya nufe shi da wata fandara da zalunci to za Mu dandana masa azaba mai radadi[1]

(26) Kuma (ka tuna) lokacin da Muka nuna wa Ibrahimu gurbin Dakin (Ka'aba, Muka ce da shi): "Kada ka hada komai da Ni (wajen bauta), kuma ka tsarkake Dakina ga masu dawafi da masu zama a cikinsa da kuma masu ruku'i masu sujjada

(27) Kuma ka yi shela cikin mutane saboda yin Hajji, za su zo maka matafiya a kasa da kuma kan kowanne rakumi mai damammen ciki, za su zo maka daga kowane wuri mai nisa

(28) Don su halarci amfanin da za su samu, kuma su ambaci sunan Allah cikin kwanaki sanannu a kan abin da Ya arzuta su da shi na dabbobin ni'ima (watau rakuma da tumaki da awakai da shanu); sai ku ci daga gare su kuma ku ciyar da galabaitaccen matalauci (29) Sannan su kammala ayyukan hajjinsu (kamar yin aski da yanke farce), kuma su cika alkawuransu (na yin hadaya da layya), kuma su yi dawafi a 'yantaccen Daki (na Ka'aba)

(30) Wannan (umarni da aka yi muku) kuwa, duk wanda ya girmama abubuwan da Allah Ya hana (a Hajji) to shi ya fi masa alheri a wurin Ubangijinsa. An kuma halatta muku dabbobin ni'ima, in ban da wadanda aka karanta muku (haramcinsu)[2]. To sai ku nisanci kazanta ta bauta wa gumaka, kuma ku nisanci fadar shaidar zur

(1) Watau kudurce niyyar aikata laifi a cikin hurumin Makka kawai ya isa ya jawo wa mutum azabar Allah ko da kuwa bai aikata ba.

(2) Watau kamar abubuwan da aka ambata muku a Suratul An'am aya ta 145; da kuma wanda aka ambata bayan saukar wannan ayar kamar na cikin Suratul Ma'ida aya ta 3.

حُنَفَآءَ لِلَّهِ غَيۡرَ مُشۡرِكِينَ بِهِۦۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَكَأَنَّمَا خَرَّ مِنَ
ٱلسَّمَآءِ فَتَخۡطَفُهُ ٱلطَّيۡرُ أَوۡ تَهۡوِي بِهِ ٱلرِّيحُ فِي مَكَانٖ سَحِيقٖ
﴿٣١﴾ ذَٰلِكَۖ وَمَن يُعَظِّمۡ شَعَٰٓئِرَ ٱللَّهِ فَإِنَّهَا مِن تَقۡوَى ٱلۡقُلُوبِ ﴿٣٢﴾
لَكُمۡ فِيهَا مَنَٰفِعُ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمًّى ثُمَّ مَحِلُّهَآ إِلَى ٱلۡبَيۡتِ ٱلۡعَتِيقِ
﴿٣٣﴾ وَلِكُلِّ أُمَّةٖ جَعَلۡنَا مَنسَكٗا لِّيَذۡكُرُواْ ٱسۡمَ ٱللَّهِ عَلَىٰ
مَا رَزَقَهُم مِّنۢ بَهِيمَةِ ٱلۡأَنۡعَٰمِۗ فَإِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞ فَلَهُۥٓ
أَسۡلِمُواْۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُخۡبِتِينَ ﴿٣٤﴾ ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَجِلَتۡ
قُلُوبُهُمۡ وَٱلصَّٰبِرِينَ عَلَىٰ مَآ أَصَابَهُمۡ وَٱلۡمُقِيمِي ٱلصَّلَوٰةِ
وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ﴿٣٥﴾ وَٱلۡبُدۡنَ جَعَلۡنَٰهَا لَكُم مِّن شَعَآئِرِ
ٱللَّهِ لَكُمۡ فِيهَا خَيۡرٞۖ فَٱذۡكُرُواْ ٱسۡمَ ٱللَّهِ عَلَيۡهَا صَوَآفَّۖ فَإِذَا وَجَبَتۡ
جُنُوبُهَا فَكُلُواْ مِنۡهَا وَأَطۡعِمُواْ ٱلۡقَانِعَ وَٱلۡمُعۡتَرَّۚ كَذَٰلِكَ سَخَّرۡنَٰهَا
لَكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ﴿٣٦﴾ لَن يَنَالَ ٱللَّهَ لُحُومُهَا وَلَا دِمَآؤُهَا
وَلَٰكِن يَنَالُهُ ٱلتَّقۡوَىٰ مِنكُمۡۚ كَذَٰلِكَ سَخَّرَهَا لَكُمۡ لِتُكَبِّرُواْ
ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا هَدَىٰكُمۡۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ﴿٣٧﴾ ۞إِنَّ ٱللَّهَ يُدَٰفِعُ
عَنِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ كُلَّ خَوَّانٖ كَفُورٍ ﴿٣٨﴾

(31) Kwa kumtakasikia Imani Allah, bila ya kumshirikisha. Na anaye mshirikisha Allah ni kama kwamba ameporomoka kutoka mbinguni, kisha ndege wakamnyakua au upepo ukamtupa pahala pa mbali

(32) Wannan kuwa (haka yake), duk wanda ya girmama wuraren ibadar (Hajji) na Allah to lalle wannan yana daga taƙawar zukata

(33) Kuna da wata moriya game da su (dabbobin)(1) har zuwa wani lokaci ƙayyadajje (shi ne lokacin yanka su), sannan kuma wurin yankansu zuwa ga Daki ne ‘yantacce (wato Harami baki ɗayansa)

(34) Kowacce al’umma kuma Mun sanya musu (irin) bautar (da za su don su ambaci sunan Allah bisa abin da Ya arzuta su da shi na dabbobin ni’ima. Sannan abin bautarku abin bauta ne guda Ɗaya, to gare Shi kawai za ku miƙa wuya. Kuma ka yi albishir ga masu ƙasƙantar da kai

(35) (Su ne kuwa) waɗanda, idan aka ambaci Allah sai zukatansu su raurawa, kuma masu haƙuri bisa abin da ya same su, kuma masu tsai da salla, kuma masu ciyarwa daga abin da Allah Ya arzuta su (da shi)

(36) (Raƙuma) kuma masu ƙiba Mun sanya muku su alamomi ne na bautar Allah; kuna da amfani game da su (na rayuwarku). To sai ku ambaci sunan Allah a kansu suna tsaye a kan ƙafa uku (lokacin soke su). To idan ransu ya fita bayan sun faɗi, sai ku ci daga gare su kuma ku ciyar da mai wadatar zuci da kuma mai bara. Kamar haka Muka hore muku su don ku yi godiya

(37) Namansu da jininsu ba sa zuwa wajen Allah, sai dai taƙawarku ce za ta isa gare Shi. Kamar haka Ya hore muku su don ku girmama Allah bisa shiryarwar da Ya yi muku (da addininsa). Kuma ka yi albishir ga masu kyautatawa

(38) Haƙiƙa Allah Yana bayar da kariya ga waɗanda suka yi imani. Lalle Allah ba Ya son duk mai ha’inci, butuluKuma ka yi albishir ga masu kyautatawa

(1) Watau za su amfana da su wajen hawansu da amfani da gashinsu da nononsu da sauransu.

أُذِنَ لِلَّذِينَ يُقَٰتَلُونَ بِأَنَّهُمْ ظُلِمُوا۟ ۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ نَصْرِهِمْ لَقَدِيرٌ ﴿٣٩﴾
ٱلَّذِينَ أُخْرِجُوا۟ مِن دِيَٰرِهِم بِغَيْرِ حَقٍّ إِلَّآ أَن يَقُولُوا۟ رَبُّنَا ٱللَّهُ ۗ وَلَوْلَا دَفْعُ ٱللَّهِ ٱلنَّاسَ بَعْضَهُم بِبَعْضٍ لَّهُدِّمَتْ
صَوَٰمِعُ وَبِيَعٌ وَصَلَوَٰتٌ وَمَسَٰجِدُ يُذْكَرُ فِيهَا ٱسْمُ ٱللَّهِ كَثِيرًا ۗ وَلَيَنصُرَنَّ ٱللَّهُ مَن يَنصُرُهُۥٓ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَقَوِىٌّ
عَزِيزٌ ﴿٤٠﴾ ٱلَّذِينَ إِن مَّكَّنَّٰهُمْ فِى ٱلْأَرْضِ أَقَامُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ
وَءَاتَوُا۟ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَمَرُوا۟ بِٱلْمَعْرُوفِ وَنَهَوْا۟ عَنِ ٱلْمُنكَرِ ۗ
وَلِلَّهِ عَٰقِبَةُ ٱلْأُمُورِ ﴿٤١﴾ وَإِن يُكَذِّبُوكَ فَقَدْ كَذَّبَتْ
قَبْلَهُمْ قَوْمُ نُوحٍ وَعَادٌ وَثَمُودُ ﴿٤٢﴾ وَقَوْمُ إِبْرَٰهِيمَ وَقَوْمُ
لُوطٍ ﴿٤٣﴾ وَأَصْحَٰبُ مَدْيَنَ ۖ وَكُذِّبَ مُوسَىٰ ۖ فَأَمْلَيْتُ لِلْكَٰفِرِينَ
ثُمَّ أَخَذْتُهُمْ ۖ فَكَيْفَ كَانَ نَكِيرِ ﴿٤٤﴾ فَكَأَيِّن مِّن قَرْيَةٍ
أَهْلَكْنَٰهَا وَهِىَ ظَالِمَةٌ فَهِىَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا وَبِئْرٍ
مُّعَطَّلَةٍ وَقَصْرٍ مَّشِيدٍ ﴿٤٥﴾ أَفَلَمْ يَسِيرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ فَتَكُونَ
لَهُمْ قُلُوبٌ يَعْقِلُونَ بِهَآ أَوْ ءَاذَانٌ يَسْمَعُونَ بِهَا ۖ فَإِنَّهَا
لَا تَعْمَى ٱلْأَبْصَٰرُ وَلَٰكِن تَعْمَى ٱلْقُلُوبُ ٱلَّتِى فِى ٱلصُّدُورِ ﴿٤٦﴾

(39) An yi izini (na yin yaƙi) ga waɗanda ake yaƙa[1] don ko lalle an zalunce su. Lalle kuma Allah Mai iko ne bisa taimakon su

(40) (Su ne) waɗanda aka fitar da su daga gidajensu ba da wani laifi ba, sai don kawai sun ce: "Allah ne Ubangijinmu". Kuma ba don kariyar Allah ga wasu mutane ta hanyar wasu ba, to da lalle an rusa wuraren bauta (na Nasara da suka ƙaurace wa 'yan'uwansu), da coci-coci da wuraren bautar Yahudawa da masallatai (na Musulmi) waɗanda ake ambaton sunan Allah da yawa a cikinsu. Kuma tabbas Allah zai taimaki mai taimakon Sa. Lalle Allah Mai ƙarfi ne, Mabuwayi

(41) (Su ne) waɗanda, idan Muka kafa su a bayan ƙasa sai su tsai da salla su kuma ba da zakka kuma su yi umarni da aikin alheri su kuma yi hani daga mummunan aiki. Karshen al'amura kuwa na Allah ne

(42) Idan kuwa suka ƙaryata ka, to haƙiƙa mutanen Nuhu da Adawa da Samudawa sun ƙaryata (manzanni) kafin su

(43) Da mutanen Ibrahimu da mutanen Luɗu (su ma sun ƙaryata)(44) Da ma mutanen Madyana (su ma sun ƙaryata); an kuma ƙaryata Musa, sai Na jinkirta wa kafurai, sannan Na kama su (da azabata); to ƙaƙa (ƙarshen) kashedina (a gare su) ya kasance?

(45) Sannan alƙarya nawa muka hallaka su alhalin suna azzalumai, sai ga su suna rugurguje a kan rufinsu sun zama kufai, da kuma rijiyoyin da aka watsar da amfani da su, da manya-manyan gine-gine da aka ɗaukaka su?

(46) Yanzu ba za su yi tafiya a bayan ƙasa ba don su samu zukata da za su riƙa tunani da su, ko kuwa kunnuwa da za su riƙa ji da su? To lalle yadda lamarin yake ba idanduna ba ne suke makancewa sai dai zukatan da suke cikin ƙiraza su ne suke makancewa

(1) Watau sahabban Annabi ( ) waɗanda kafirai a lokacin suke yaƙar su.

وَيَسْتَعْجِلُونَكَ بِٱلْعَذَابِ وَلَن يُخْلِفَ ٱللَّهُ وَعْدَهُۥ ۚ وَإِنَّ يَوْمًا
عِندَ رَبِّكَ كَأَلْفِ سَنَةٍ مِّمَّا تَعُدُّونَ ﴿٤٧﴾ وَكَأَيِّن مِّن
قَرْيَةٍ أَمْلَيْتُ لَهَا وَهِىَ ظَالِمَةٌ ثُمَّ أَخَذْتُهَا وَإِلَىَّ ٱلْمَصِيرُ
﴿٤٨﴾ قُلْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّمَآ أَنَا۠ لَكُمْ نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿٤٩﴾ فَٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُم مَّغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ كَرِيمٌ ﴿٥٠﴾
وَٱلَّذِينَ سَعَوْا۟ فِىٓ ءَايَٰتِنَا مُعَٰجِزِينَ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ
ٱلْجَحِيمِ ﴿٥١﴾ وَمَآ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ مِن رَّسُولٍ وَلَا نَبِىٍّ إِلَّآ
إِذَا تَمَنَّىٰٓ أَلْقَى ٱلشَّيْطَٰنُ فِىٓ أُمْنِيَّتِهِۦ فَيَنسَخُ ٱللَّهُ مَا يُلْقِى
ٱلشَّيْطَٰنُ ثُمَّ يُحْكِمُ ٱللَّهُ ءَايَٰتِهِۦ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿٥٢﴾ لِّيَجْعَلَ
مَا يُلْقِى ٱلشَّيْطَٰنُ فِتْنَةً لِّلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ وَٱلْقَاسِيَةِ
قُلُوبُهُمْ ۗ وَإِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ لَفِى شِقَاقٍۭ بَعِيدٍ ﴿٥٣﴾ وَلِيَعْلَمَ
ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْعِلْمَ أَنَّهُ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَيُؤْمِنُوا۟ بِهِۦ
فَتُخْبِتَ لَهُۥ قُلُوبُهُمْ ۗ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهَادِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِلَىٰ صِرَٰطٍ
مُّسْتَقِيمٍ ﴿٥٤﴾ وَلَا يَزَالُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ فِى مِرْيَةٍ مِّنْهُ حَتَّىٰ
تَأْتِيَهُمُ ٱلسَّاعَةُ بَغْتَةً أَوْ يَأْتِيَهُمْ عَذَابُ يَوْمٍ عَقِيمٍ ﴿٥٥﴾

(47) Kuma suna neman ka da gaggauto musu da azaba, Allah kuwa ba Ya saɓa alƙawarinsa. Lalle kuma yini ɗaya a wurin Ubangijinka kamar shekara dubu ne daga irin waɗanda kuke ƙirgawa
(48) Kuma alƙaryu nawa ne Na saurara musu, alhali kuwa suna kafirai, sannan (daga baya) Na kama su? Makoma kuma zuwa gare Ni ne
(49) Ka ce: "Ya ku mutane, ni dai kawai mai gargaɗi ne a gare ku mai bayyana (gargaɗi)."
(50) To waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki na gari, suna da gafara da kuma arziki mai girma
(51)Waɗanda kuwa suka yi iya ƙoƙarinsu game da ɓata ayoyinmu suna ganin za su gagare Mu, to waɗannan su ne ma'abota (wutar) Jahima
(52) Kuma babu wani manzo ko wani annabi[1] da Muka aiko a gabaninka face idan ya yi karatu sai Shaiɗan ya jefa (ruɗu da wasiwasi) cikin karatunsa; sannan Allah Yakan ɓata abin da shi Shaiɗan yake jefawa, sannan Allah Ya tabbatar da ayoyinsa. Allah kuwa Masani ne Mai hikima
(53) (Yakan yi haka ne) don Ya sanya abin da Shaiɗan yake jefawa ya zama fitina ga waɗanda suke da cuta a cikin zukatansu, da kuma masu ƙeƙasassun zukata. Lalle kuma azzalumai tabbas suna cikin saɓani mai nisa
(54) Don kuma waɗanda aka bai wa ilimi su san cewa shi (Alƙur'ani) gaskiya ne daga Ubangijinka yake, sai su yi imani da shi sai zukatansu su nutsu da shi. Kuma lalle Allah tabbas Mai shiryar da waɗanda suka yi imani ne zuwa ga tafarki madaidaici
(55) Waɗanda kuwa suka kafirce ba za su daina kokwanton sa ba (watau Alƙur'ani) har sai alƙiyama ta zo musu ba zato ba tsammani, ko kuma azabar rana bakarara[2] ta zo musu .

(1) Manzo, shi ne wanda Allah ( ) ya aika shi zuwa ga kafirai 'yan jahiliyya. Annabi kuwa shi ne wanda ya aika shi zuwa ga mutanen da ba 'yan jahiliyya ba, amma suna da buƙatar a jaddada musu addininsu.

(2) Watau ranar da kafirai ba za su samu wata rahama ko wani alheri ba.

ٱلْمُلْكُ يَوْمَئِذٍ لِّلَّهِ يَحْكُمُ بَيْنَهُمْ ۚ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟
وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فِى جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ﴿٥٦﴾ وَٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ وَكَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا فَأُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ
مُّهِينٌ ﴿٥٧﴾ وَٱلَّذِينَ هَاجَرُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ثُمَّ قُتِلُوٓا۟
أَوْ مَاتُوا۟ لَيَرْزُقَنَّهُمُ ٱللَّهُ رِزْقًا حَسَنًا ۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهُوَ
خَيْرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ﴿٥٨﴾ لَيُدْخِلَنَّهُم مُّدْخَلًا يَرْضَوْنَهُۥ ۗ
وَإِنَّ ٱللَّهَ لَعَلِيمٌ حَلِيمٌ ﴿٥٩﴾ ۞ ذَٰلِكَ ۖ وَمَنْ عَاقَبَ بِمِثْلِ
مَا عُوقِبَ بِهِۦ ثُمَّ بُغِىَ عَلَيْهِ لَيَنصُرَنَّهُ ٱللَّهُ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ
لَعَفُوٌّ غَفُورٌ ﴿٦٠﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ يُولِجُ ٱلَّيْلَ فِى
ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِى ٱلَّيْلِ وَأَنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌۢ
بَصِيرٌ ﴿٦١﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْحَقُّ وَأَنَّ مَا يَدْعُونَ
مِن دُونِهِۦ هُوَ ٱلْبَٰطِلُ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْعَلِىُّ ٱلْكَبِيرُ ﴿٦٢﴾
أَلَمْ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَتُصْبِحُ ٱلْأَرْضُ
مُخْضَرَّةً ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَطِيفٌ خَبِيرٌ ﴿٦٣﴾ لَّهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهُوَ ٱلْغَنِىُّ ٱلْحَمِيدُ ﴿٦٤﴾

(56) Mulki a wannan ranar na Allah ne, zai yi hukunci a tsakaninsu. To waɗanda suka yi imani suka kuma yi kyawawan ayyuka, suna cikin gidajen Aljanna na ni'ima
(57) Waɗanda kuwa suka kafirta suka kuma ƙaryata ayoyinmu, to waɗannan suna da azaba mai wulaƙantawa
(58) Waɗanda kuwa suka yi hijira saboda Allah sannan aka kashe su ko kuma suka mutu, to lalle Allah tabbas zai arzuta su da kyakkyawan arziki. Kuma lalle Allah tabbas Shi ne Fiyayyen masu arzutawa
(59) Lalle tabbas Zai shigar da su wata mashiga da za su yarda da ita. Kuma lalle Allah tabbas Masani ne, Mai hakuri
(60) Wannan (abu da aka ambata haka yake), duk wanda ya yi uƙuba da irin abin da aka yi masa uƙuba da shi, sannan aka daɗa yi masa ta'addanci, to lalle Allah tabbas zai taimake shi. Lalle Allah tabbas Mai afuwa ne, Mai gafara
(61) Wannan (taimakon kuwa zai kasance ne) saboda lalle Allah Shi Yake shigar da dare cikin rana, Yake kuma shigar da rana cikin dare, kuma lalle Allah Mai ji ne, Mai gani
(62) Wannan kuwa saboda lalle Allah Shi ne (abin bauta) na gaskiya, kuma lalle abin da suke bauta wa wanda ba Shi ba shi na ƙarya ne, kuma lalle Allah Shi ne Maɗaukaki, Mai girma
(63) Shin ba ka ga cewa Allah ne Ya saukar da ruwa daga sama ba, sai ƙasa ta zama koriya shar? Lalle Allah Mai tausasawa ne, Masani
(64) Abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nasa ne. Kuma lalle Allah tabbas Shi ne Mawadaci, Sha-Yabo

أَلَمْ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ سَخَّرَ لَكُم مَّا فِى ٱلْأَرْضِ وَٱلْفُلْكَ تَجْرِى
فِى ٱلْبَحْرِ بِأَمْرِهِۦ ۖ وَيُمْسِكُ ٱلسَّمَآءَ أَن تَقَعَ عَلَى ٱلْأَرْضِ إِلَّا
بِإِذْنِهِۦٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِٱلنَّاسِ لَرَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿٦٥﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى
أَحْيَاكُمْ ثُمَّ يُمِيتُكُمْ ثُمَّ يُحْيِيكُمْ ۗ إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لَكَفُورٌ ﴿٦٦﴾
لِّكُلِّ أُمَّةٍ جَعَلْنَا مَنسَكًا هُمْ نَاسِكُوهُ ۖ فَلَا يُنَٰزِعُنَّكَ
فِى ٱلْأَمْرِ ۘ وَٱدْعُ إِلَىٰ رَبِّكَ ۖ إِنَّكَ لَعَلَىٰ هُدًى مُّسْتَقِيمٍ ﴿٦٧﴾
وَإِن جَٰدَلُوكَ فَقُلِ ٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿٦٨﴾ ٱللَّهُ يَحْكُمُ
بَيْنَكُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فِيمَا كُنتُمْ فِيهِ تَخْتَلِفُونَ ﴿٦٩﴾
أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِى ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ ۗ إِنَّ
ذَٰلِكَ فِى كِتَٰبٍ ۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ ﴿٧٠﴾ وَيَعْبُدُونَ
مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِۦ سُلْطَٰنًا وَمَا لَيْسَ لَهُم بِهِۦ
عِلْمٌ ۗ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِن نَّصِيرٍ ﴿٧١﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا
بَيِّنَٰتٍ تَعْرِفُ فِى وُجُوهِ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ٱلْمُنكَرَ ۖ يَكَادُونَ
يَسْطُونَ بِٱلَّذِينَ يَتْلُونَ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتِنَا ۗ قُلْ أَفَأُنَبِّئُكُم بِشَرٍّ مِّن
ذَٰلِكُمُ ۖ ٱلنَّارُ وَعَدَهَا ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ۖ وَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ﴿٧٢﴾

(65) Shin ba ka ga cewa Allah Ya hore muku abin da yake cikin ƙasa, da kuma jiragen ruwa da suke gudu a cikin kogi da umarninsa, kuma Yake rike sama don kada ta faɗo a kan ƙasa, sai da izininsa? Lalle Allah Mai tausayi ne, Mai rahama ga mutane

(66) Shi ne kuma Wanda Ya raya ku sannan zai kashe ku sannan Ya (sake) raya ku. Lalle mutum tabbas mai yawan butulci ne

(67) Kowacce al'umma Mun sanya mata hanyar (shari'a) da za su yi aiki da ita; to lalle kada su yi jayayya da kai game da lamarin (addini). Kuma ka yi kira zuwa ga (addinin) Ubangijinka; lalle kai tabbas kana bisa shiriya madaidaiciya

(68) Idan kuwa suka yi maka jayayya, sai ka ce: "Allah ne Ya fi sanin abin da kuke aikatawa."

(69) Allah zai yi hukunci a tsakaninku ranar alƙiyama game da abin da kuka kasance kuna sassaɓawa a kansa

(70) Shin ba ka sani ba cewa lalle Allah Yana sane da abin da yake cikin sama da wanda yake ƙasa? Lalle wannan yana cikin littafi (wato Lauhul-Mahafuzu). Lalle wannan mai sauƙi ne a wurin Allah

(71) Suna kuma bauta wa wanda ba Allah ba, abin da bai saukar da wani dalili ba game da shi, da kuma abin da ba su da ilimi game da shi. Azzalumai kuwa ba su da wani mataimaki

(72) Idan kuma ana karanta musu ayoyinmu bayyanannu, to za ka ga alamar musantawa a fuskokin waɗanda suka kafirta, suna kamar za su auka wa waɗanda suke karanta musu ayoyinmu. To ka ce: "Shin ba na ba ku labarin abin da ya fi wannan muni ba[1]? Wuta ce da Allah Ya yi alƙawari ga waɗanda suka kafirta; makoma kuwa ta munana."

(1) Watau fiye da abin da suke ganin muninsa idan ana karanta musu shi, watau ayoyin Alƙur'ani.

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ضُرِبَ مَثَلٌ فَٱسْتَمِعُوا۟ لَهُۥٓ ۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ
تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ لَن يَخْلُقُوا۟ ذُبَابًا وَلَوِ ٱجْتَمَعُوا۟ لَهُۥ ۖ
وَإِن يَسْلُبْهُمُ ٱلذُّبَابُ شَيْـًٔا لَّا يَسْتَنقِذُوهُ مِنْهُ ۚ ضَعُفَ
ٱلطَّالِبُ وَٱلْمَطْلُوبُ ﴿٧٣﴾ مَا قَدَرُوا۟ ٱللَّهَ حَقَّ قَدْرِهِۦٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ
لَقَوِىٌّ عَزِيزٌ ﴿٧٤﴾ ٱللَّهُ يَصْطَفِى مِنَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلًا
وَمِنَ ٱلنَّاسِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌۢ بَصِيرٌ ﴿٧٥﴾ يَعْلَمُ مَا بَيْنَ
أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ ۚ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرْجَعُ ٱلْأُمُورُ ﴿٧٦﴾ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱرْكَعُوا۟ وَٱسْجُدُوا۟ وَٱعْبُدُوا۟ رَبَّكُمْ
وَٱفْعَلُوا۟ ٱلْخَيْرَ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿٧٧﴾ وَجَٰهِدُوا۟ فِى
ٱللَّهِ حَقَّ جِهَادِهِۦ ۚ هُوَ ٱجْتَبَىٰكُمْ وَمَا جَعَلَ عَلَيْكُمْ
فِى ٱلدِّينِ مِنْ حَرَجٍ ۚ مِّلَّةَ أَبِيكُمْ إِبْرَٰهِيمَ ۚ هُوَ سَمَّىٰكُمُ
ٱلْمُسْلِمِينَ مِن قَبْلُ وَفِى هَٰذَا لِيَكُونَ ٱلرَّسُولُ شَهِيدًا عَلَيْكُمْ
وَتَكُونُوا۟ شُهَدَآءَ عَلَى ٱلنَّاسِ ۚ فَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ
وَٱعْتَصِمُوا۟ بِٱللَّهِ هُوَ مَوْلَىٰكُمْ ۖ فَنِعْمَ ٱلْمَوْلَىٰ وَنِعْمَ ٱلنَّصِيرُ ﴿٧٨﴾

سُورَةُ المُؤمِنُون

(73) Ya ku mutane, an ba da misali, to sai ku saurare shi. Lalle wadanda kuke bauta wa ba Allah ba, ba za su taba iya halittar kuda ba, ko da sun taru domin (halitta) shi; idan kuma da kudan zai cire musu (su gumakan) wani abu, to ba za su iya kwato shi ba daga wurinsa. Wanda yake nema da wanda ake nema (duka) sun yi rauni!

(74) Ba su girmama Allah ba kamar yadda ya kamata su girmama Shi. Lalle Allah tabbas Kakkarfa ne, Mabuwayi

(75) Allah Yana zabar manzanni daga mala'iku kuma daga mutane. Lalle Allah Mai ji ne, Mai gani

(76) Yana sane da abin da yake gabansu da abin da yake bayansu. Zuwa ga Allah ne kawai ake komar da al'amura

(77) Ya ku wadanda suka yi imani, ku yi ruku'i kuma ku yi sujjada, ku kuma bauta wa Ubangijinku, kuma ku aikata alheri don ku rabauta

(78) Kuma ku yi jihadi wajen (daukaka addinin) Allah iyakar iyawarku. Shi ne Ya zabe ku, bai kuma sanya muku wani kunci ba cikin addini. Addinin Babanku ne Ibrahimu. (Allah) Shi ne Ya kira ku Musulmi tuntuni, da kuma cikin wannan (Alkur'ani) don Manzo ya zama shaida a gare ku, ku kuma ku zama shaida ga (sauran) mutane. To sai ku tsai da salla kuma ku ba da zakka, ku kuma yi riko da (addinin) Allah, Shi ne Majibincin al'amarinku; to madalla da Majibinci, kuma madalla da Mataimaki

Sura Mu'uminun

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قَدْ أَفْلَحَ ٱلْمُؤْمِنُونَ ﴿١﴾ ٱلَّذِينَ هُمْ فِى صَلَاتِهِمْ خَٰشِعُونَ
﴿٢﴾ وَٱلَّذِينَ هُمْ عَنِ ٱللَّغْوِ مُعْرِضُونَ ﴿٣﴾ وَٱلَّذِينَ هُمْ لِلزَّكَوٰةِ
فَٰعِلُونَ ﴿٤﴾ وَٱلَّذِينَ هُمْ لِفُرُوجِهِمْ حَٰفِظُونَ ﴿٥﴾ إِلَّا عَلَىٰٓ
أَزْوَٰجِهِمْ أَوْ مَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُهُمْ فَإِنَّهُمْ غَيْرُ مَلُومِينَ ﴿٦﴾ فَمَنِ
ٱبْتَغَىٰ وَرَآءَ ذَٰلِكَ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْعَادُونَ ﴿٧﴾ وَٱلَّذِينَ هُمْ
لِأَمَٰنَٰتِهِمْ وَعَهْدِهِمْ رَٰعُونَ ﴿٨﴾ وَٱلَّذِينَ هُمْ عَلَىٰ صَلَوَٰتِهِمْ
يُحَافِظُونَ ﴿٩﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْوَٰرِثُونَ ﴿١٠﴾ ٱلَّذِينَ يَرِثُونَ
ٱلْفِرْدَوْسَ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿١١﴾ وَلَقَدْ خَلَقْنَا ٱلْإِنسَٰنَ مِن
سُلَٰلَةٍ مِّن طِينٍ ﴿١٢﴾ ثُمَّ جَعَلْنَٰهُ نُطْفَةً فِى قَرَارٍ مَّكِينٍ ﴿١٣﴾
ثُمَّ خَلَقْنَا ٱلنُّطْفَةَ عَلَقَةً فَخَلَقْنَا ٱلْعَلَقَةَ مُضْغَةً فَخَلَقْنَا
ٱلْمُضْغَةَ عِظَٰمًا فَكَسَوْنَا ٱلْعِظَٰمَ لَحْمًا ثُمَّ أَنشَأْنَٰهُ خَلْقًا
ءَاخَرَ ۚ فَتَبَارَكَ ٱللَّهُ أَحْسَنُ ٱلْخَٰلِقِينَ ﴿١٤﴾ ثُمَّ إِنَّكُم بَعْدَ ذَٰلِكَ
لَمَيِّتُونَ ﴿١٥﴾ ثُمَّ إِنَّكُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ تُبْعَثُونَ ﴿١٦﴾ وَلَقَدْ
خَلَقْنَا فَوْقَكُمْ سَبْعَ طَرَآئِقَ وَمَا كُنَّا عَنِ ٱلْخَلْقِ غَٰفِلِينَ ﴿١٧﴾

(1) Hakika muminai sun rabauta
(2) (Su ne) wadanda suke masu kaskantar da kai a cikin sallarsu
(3) Kuma wadanda suke masu kau da kai daga yasasshiyar magana
(4) Kuma wadanda suke masu aiwatar da zakka
(5) Kuma wadanda suke masu kiyaye farjinsu
(6) Sai dai ga matayensu ko kuma kwara-kwaransu, to lalle su ba abin zargi ba ne
(7) Sannan duk wanda ya nemi (wata hanya) ba wadannan ba, to wadannan su ne masu ketare iyaka
(8) Kuma wadanda suke masu kiyaye amanarsu da kuma alkawarinsu
(9) Kuma wadanda suke kiyaye sallolinsu(10) Wadannan su ne magada
(11) Wadanda suke gadar (Aljannar) Firdausi, su madawwama ne a cikinta
(12) Kuma hakika Mun halicci mutum daga tataccen tabo
(13) Sannan Muka mai da shi maniyyi cikin wuri amintacce
(14) Sannan Muka mayar da maniyyin ya zama gudan jini, sai gudan jinin ya zama tsoka, sai Muka mai da tsokar kasusuwa, sannan Muka lulluɓe kasusuwan da nama, sannan kuma Muka mai da shi wata halitta daban. To albarkatun Allah sun yawaita, Wanda Shi ne Mafi gwanintar masu halitta
(15) Sannan kuma lalle tabbas bayan haka za ku mutu(16) Sannan kuma hakika za a tashe ku ranar Alkiyama
(17) Kuma hakika Mun halicci hanyoyi bakwai a sama da ku, ba Mu kuma zama gafalallu ba game da halittar

وَأَنزَلْنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءًۢ بِقَدَرٍ فَأَسْكَنَّٰهُ فِى ٱلْأَرْضِ ۖ وَإِنَّا عَلَىٰ
ذَهَابٍۭ بِهِۦ لَقَٰدِرُونَ ﴿١٨﴾ فَأَنشَأْنَا لَكُم بِهِۦ جَنَّٰتٍ مِّن نَّخِيلٍ
وَأَعْنَٰبٍ لَّكُمْ فِيهَا فَوَٰكِهُ كَثِيرَةٌ وَمِنْهَا تَأْكُلُونَ ﴿١٩﴾ وَشَجَرَةً
تَخْرُجُ مِن طُورِ سَيْنَآءَ تَنۢبُتُ بِٱلدُّهْنِ وَصِبْغٍ لِّلْءَاكِلِينَ ﴿٢٠﴾
وَإِنَّ لَكُمْ فِى ٱلْأَنْعَٰمِ لَعِبْرَةً ۖ نُّسْقِيكُم مِّمَّا فِى بُطُونِهَا وَلَكُمْ فِيهَا
مَنَٰفِعُ كَثِيرَةٌ وَمِنْهَا تَأْكُلُونَ ﴿٢١﴾ وَعَلَيْهَا وَعَلَى ٱلْفُلْكِ تُحْمَلُونَ
﴿٢٢﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوْمِهِۦ فَقَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ
مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥٓ ۚ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿٢٣﴾ فَقَالَ ٱلْمَلَؤُا۟ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ مِن قَوْمِهِۦ مَا هَٰذَآ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ يُرِيدُ أَن يَتَفَضَّلَ عَلَيْكُمْ
وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ لَأَنزَلَ مَلَٰٓئِكَةً مَّا سَمِعْنَا بِهَٰذَا فِىٓ ءَابَآئِنَا
ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٢٤﴾ إِنْ هُوَ إِلَّا رَجُلٌۢ بِهِۦ جِنَّةٌ فَتَرَبَّصُوا۟ بِهِۦ حَتَّىٰ حِينٍ
﴿٢٥﴾ قَالَ رَبِّ ٱنصُرْنِى بِمَا كَذَّبُونِ ﴿٢٦﴾ فَأَوْحَيْنَآ إِلَيْهِ أَنِ ٱصْنَعِ
ٱلْفُلْكَ بِأَعْيُنِنَا وَوَحْيِنَا فَإِذَا جَآءَ أَمْرُنَا وَفَارَ ٱلتَّنُّورُ فَٱسْلُكْ
فِيهَا مِن كُلٍّ زَوْجَيْنِ ٱثْنَيْنِ وَأَهْلَكَ إِلَّا مَن سَبَقَ عَلَيْهِ
ٱلْقَوْلُ مِنْهُمْ ۖ وَلَا تُخَٰطِبْنِى فِى ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓا۟ ۖ إِنَّهُم مُّغْرَقُونَ ﴿٢٧﴾

(18) Muka kuma saukar da ruwa daga sama daidai gwargwado, sai Muka zaunar da shi a cikin ƙasa, kuma lalle Mu Masu iko ne a kan kawar da shi

(19) Sai Muka samar muku gonaki na dabinai da inabai da shi (ruwan), kuna kuma da kayan marmari masu yawa a cikinsu (gonakin), kuma daga gare su kuke ci

(20) Kuma (Mun halitta muku) wata bishiya da take fitowa a (dutsen) Ɗuri Sina'a, tana fito da man (zaitun) kuma mahaɗin abinci ne

(21) Kuma lalle akwai izina a gare ku game da dabbobin ni'ima[1]; Muna shayar da ku daga abin da yake cikinsu[2], kuma kuna da amfani mai yawa daga gare su, daga gare su kuma kuke ci

(22) A kansu da kuma a kan jirgin ruwa ake ɗaukar ku

(23) Haƙiƙa kuma Mun aiko Nuhu zuwa ga mutanensa, sai ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta in ba Shi ba; me ya sa ne ba za ku yi taƙawa ba."

(24) Sai manya-manyan da suka kafirce daga mutanen nasa suka ce: "Ai wannan ba kowa ba ne face mutum irinku, yana so ne ya samu fifiko a kanku, kuma da Allah Ya ga dama da sai Ya saukar da mala'iku, mu ba mu taɓa jin irin wannan ba daga iyayenmu na farko

(25) "Ba kowa ba ne shi in ban da mutum da yake da (taɓin) aljan, sai ku saurara masa har zuwa wani ɗan lokaci."

(26) Ya ce: "Ubangijina Ka taimake ni game da abin da suka ƙaryata ni a kansa."

(27) Sai Muka yiwo masa wahayi cewa: "Ka sassaƙa jirgin ruwa a ƙarƙashin kulawarmu da umarninmu, sannan idan umarninmu (na hallaka su) ya zo, kuma tanderu ya ɓuɓɓugo da ruwa, sai ka saka ma'aurata guda biyu daga kowane jinsi a cikinsa, da kuma iyalanka, sai wanda kalmar (halaka) ta rigaya a kansa daga cikinsu; kuma kada ka ce min komai game da waɗanda suka kafirta; lalle su waɗanda za a nutsar ne

(1) Su ne raƙuma da shanu da tumaki da awaki.

(2) Shi ne tataccen nono.

فَإِذَا ٱسْتَوَيْتَ أَنتَ وَمَن مَّعَكَ عَلَى ٱلْفُلْكِ فَقُلِ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِى
نَجَّىٰنَا مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٢٨﴾ وَقُل رَّبِّ أَنزِلْنِى مُنزَلًا مُّبَارَكًا وَأَنتَ
خَيْرُ ٱلْمُنزِلِينَ ﴿٢٩﴾ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ وَإِن كُنَّا لَمُبْتَلِينَ ﴿٣٠﴾ ثُمَّ أَنشَأْنَا
مِنۢ بَعْدِهِمْ قَرْنًا ءَاخَرِينَ ﴿٣١﴾ فَأَرْسَلْنَا فِيهِمْ رَسُولًا مِّنْهُمْ أَنِ ٱعْبُدُوا۟
ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥٓ ۚ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿٣٢﴾ وَقَالَ ٱلْمَلَأُ مِن قَوْمِهِ
ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَكَذَّبُوا۟ بِلِقَآءِ ٱلْءَاخِرَةِ وَأَتْرَفْنَٰهُمْ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا
مَا هَٰذَآ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ يَأْكُلُ مِمَّا تَأْكُلُونَ مِنْهُ وَيَشْرَبُ
مِمَّا تَشْرَبُونَ ﴿٣٣﴾ وَلَئِنْ أَطَعْتُم بَشَرًا مِّثْلَكُمْ إِنَّكُمْ إِذًا لَّخَٰسِرُونَ
﴿٣٤﴾ أَيَعِدُكُمْ أَنَّكُمْ إِذَا مِتُّمْ وَكُنتُمْ تُرَابًا وَعِظَٰمًا أَنَّكُم مُّخْرَجُونَ
﴿٣٥﴾ هَيْهَاتَ هَيْهَاتَ لِمَا تُوعَدُونَ ﴿٣٦﴾ إِنْ هِىَ إِلَّا حَيَاتُنَا
ٱلدُّنْيَا نَمُوتُ وَنَحْيَا وَمَا نَحْنُ بِمَبْعُوثِينَ ﴿٣٧﴾ إِنْ هُوَ إِلَّا
رَجُلٌ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا وَمَا نَحْنُ لَهُۥ بِمُؤْمِنِينَ ﴿٣٨﴾ قَالَ رَبِّ
ٱنصُرْنِى بِمَا كَذَّبُونِ ﴿٣٩﴾ قَالَ عَمَّا قَلِيلٍ لَّيُصْبِحُنَّ نَٰدِمِينَ ﴿٤٠﴾
فَأَخَذَتْهُمُ ٱلصَّيْحَةُ بِٱلْحَقِّ فَجَعَلْنَٰهُمْ غُثَآءً ۚ فَبُعْدًا لِّلْقَوْمِ
ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٤١﴾ ثُمَّ أَنشَأْنَا مِنۢ بَعْدِهِمْ قُرُونًا ءَاخَرِينَ ﴿٤٢﴾

(28) "To idan kai da waɗanda suke tare da kai kuka daidaita a kan jirgin, sai ka ce: "Na gode wa Allah wanda Ya tserar da mu daga mutane azzalumai."
(29) Kuma ka ce: "Ubangijina Ka saukar da ni masauki mai albarka, Kai ne kuwa Fiyayyen masu saukarwa."
(30) Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi, Mu kuma haƙiƙa Mun kasance Masu jarrabawa ne
(31) Sannan kuma a bayansu Muka halicci wata al'umma daban
(32) Sai Muka aiko musu wani manzon daga cikinsu da cewa:

"Ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta in ba Shi ba; me ya sa ne ba za ku yi taƙawa ba?"
(33) Kuma manyan mutane daga cikin mutanensa waɗanda suka kafirce suka kuma ƙaryata haɗuwa da ranar lahira, Muka kuma wadata su a rayuwar duniya, suka ce: "Wannan ba kowa ba ne face mutum kamarku, yana cin irin abin da kuke ci, yana kuma shan irin abin da kuke sha
(34) "Kuma tabbas in har kuka bi mutum kamarku, to lalle tabbas a sannan kun yi asara
(35) ¿"Shin yanzu ya riƙa yi muku alƙawarin cewa idan kun mutu kun kuma zama turɓaya da ƙasusuwa cewa lalle za a tashe ku?"
(36) "Faufau-faufau game da abin da ake yi muku alƙawarinsa!
(37) "Ba mu da wata (rayuwa) sai rayuwarmu ta duniya; mu mutu kuma mu rayu, ba kuwa za a tashe mu (daga ƙaburburanmu) ba.
(38) "Shi ba kowa ba ne face mutum da ya ƙaga wa Allah ƙarya, mu kuwa ba za mu yi imani da shi ba."
(39) Ya ce: "Ya Ubangijina, Ka taimake ni game da abin da suke ƙaryata ni a kansa."
(40) Ya ce: "Ba da daɗewa ba tabbas za su wayi gari suna masu nadama."
(41) Sai tsawa ta far musu bisa cancanta, sai Muka mai da su dudduga. To nisanta (daga rahamar Allah) ta tabbata ga mutane azzalumai
(42) Sannan kuma a bayansu Muka halitta wasu al'ummun daban

مَا تَسْبِقُ مِنْ أُمَّةٍ أَجَلَهَا وَمَا يَسْتَـْٔخِرُونَ ﴿٤٣﴾ ثُمَّ أَرْسَلْنَا رُسُلَنَا
تَتْرَا ۖ كُلَّ مَا جَآءَ أُمَّةً رَّسُولُهَا كَذَّبُوهُ ۖ فَأَتْبَعْنَا بَعْضَهُم بَعْضًا
وَجَعَلْنَٰهُمْ أَحَادِيثَ ۚ فَبُعْدًا لِّقَوْمٍ لَّا يُؤْمِنُونَ ﴿٤٤﴾ ثُمَّ أَرْسَلْنَا مُوسَىٰ
وَأَخَاهُ هَٰرُونَ بِـَٔايَٰتِنَا وَسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿٤٥﴾ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِۦ
فَٱسْتَكْبَرُوا۟ وَكَانُوا۟ قَوْمًا عَالِينَ ﴿٤٦﴾ فَقَالُوٓا۟ أَنُؤْمِنُ لِبَشَرَيْنِ مِثْلِنَا
وَقَوْمُهُمَا لَنَا عَٰبِدُونَ ﴿٤٧﴾ فَكَذَّبُوهُمَا فَكَانُوا۟ مِنَ ٱلْمُهْلَكِينَ
﴿٤٨﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ لَعَلَّهُمْ يَهْتَدُونَ ﴿٤٩﴾ وَجَعَلْنَا
ٱبْنَ مَرْيَمَ وَأُمَّهُۥٓ ءَايَةً وَءَاوَيْنَٰهُمَآ إِلَىٰ رَبْوَةٍ ذَاتِ قَرَارٍ وَمَعِينٍ
﴿٥٠﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلرُّسُلُ كُلُوا۟ مِنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَٱعْمَلُوا۟ صَٰلِحًا ۖ إِنِّى بِمَا
تَعْمَلُونَ عَلِيمٌ ﴿٥١﴾ وَإِنَّ هَٰذِهِۦٓ أُمَّتُكُمْ أُمَّةً وَٰحِدَةً وَأَنَا۠ رَبُّكُمْ
فَٱتَّقُونِ ﴿٥٢﴾ فَتَقَطَّعُوٓا۟ أَمْرَهُم بَيْنَهُمْ زُبُرًا ۖ كُلُّ حِزْبٍۭ بِمَا لَدَيْهِمْ
فَرِحُونَ ﴿٥٣﴾ فَذَرْهُمْ فِى غَمْرَتِهِمْ حَتَّىٰ حِينٍ ﴿٥٤﴾ أَيَحْسَبُونَ أَنَّمَا نُمِدُّهُم
بِهِۦ مِن مَّالٍ وَبَنِينَ ﴿٥٥﴾ نُسَارِعُ لَهُمْ فِى ٱلْخَيْرَٰتِ ۚ بَل لَّا يَشْعُرُونَ
﴿٥٦﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ هُم مِّنْ خَشْيَةِ رَبِّهِم مُّشْفِقُونَ ﴿٥٧﴾ وَٱلَّذِينَ هُم
بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمْ يُؤْمِنُونَ ﴿٥٨﴾ وَٱلَّذِينَ هُم بِرَبِّهِمْ لَا يُشْرِكُونَ ﴿٥٩﴾

(43) Babu wata al'umma da take rigayar ajalinta, babu kuma wadda take jinkiri(44) Sannan Muka aiko manzanninmu suna biye da juna; duk sanda manzon (kowacce) al'umma ya zo musu sai su ƙaryata shi. Sai Muka hallaka su ɗaya bayan ɗaya, Muka kuma mai da su tarihi. To nisanta (daga rahamar Allah) ta tabbata ga mutanen da ba sa yin imani

(45) Sannan Muka aiko Musa da ɗan'uwansa Haruna da ayoyinmu da kuma hujja bayyananniya

(46) Zuwa ga Fir'auna da manyan ('yan majalisarsa), sai suka yi girman kai kuma suka kasance mutane masu haike wa (jama'a da zalunci)

(47) Sai suka ce: "Yanzu ma ba da gaskiya da mutum biyu irinmu, alhali kuwa mutanensu masu yi mana bauta ne?"

(48) Sai suka ƙaryata su (wato Musa da Haruna), sannan suka kasance daga waɗanda aka hallaka

(49) Haƙiƙa kuma Mun bai wa Musa Littafi (wato Attaura) don su shiriya

(50) Muka kuma sanya Ɗan Maryamu da mahaifiyarsa (don su zama) aya, Muka kuma zaunar da su a wata jigawa ta hutawa da kuma ruwa mai gudana

(51) Ya ku manzanni, ku ci daga halal, kuma ku yi aiki na gari; Lalle Ni ina sane da abin da kuke aikatawa

(52) Kuma lalle wannan addininku ne, addini guda ɗaya (wato Musulunci), kuma Ni ne Ubangijinku, sai ku kiyaye dokokina

(53) Sai suka sassaɓa al'amarinsu a tsakaninsu (suka kasu) ƙungiya-ƙungiya; kowacce ƙungiya tana alfahari da nata

(54) Sai ka bar su cikin ɗimuwarsu har zuwa ɗan wani lokaci

(55) Yanzu suna tsammanin cewa abin da Muke ba su na dukiya da 'ya'yaye (a duniya)

(56) Muna gaggauto musu sakamakon alheri ne? Ba haka ba ne; su dai ba sa ganewa ne

(57) Lalle waɗanda su suke cike da tsoron Ubangijinsu


(58) Kuma waɗanda suke imani da ayoyin Ubangijinsu

(59) Kuma waɗanda ba sa shirka da Ubangijinsu

وَٱلَّذِينَ يُؤْتُونَ مَآ ءَاتَواْ وَّقُلُوبُهُمْ وَجِلَةٌ أَنَّهُمْ إِلَىٰ رَبِّهِمْ رَٰجِعُونَ ﴿٦٠﴾
أُوْلَٰٓئِكَ يُسَٰرِعُونَ فِى ٱلْخَيْرَٰتِ وَهُمْ لَهَا سَٰبِقُونَ ﴿٦١﴾ وَلَا نُكَلِّفُ
نَفْسًا إِلَّا وُسْعَهَا ۚ وَلَدَيْنَا كِتَٰبٌ يَنطِقُ بِٱلْحَقِّ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ
﴿٦٢﴾ بَلْ قُلُوبُهُمْ فِى غَمْرَةٍ مِّنْ هَٰذَا وَلَهُمْ أَعْمَٰلٌ مِّن دُونِ ذَٰلِكَ
هُمْ لَهَا عَٰمِلُونَ ﴿٦٣﴾ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَخَذْنَا مُتْرَفِيهِم بِٱلْعَذَابِ إِذَا هُمْ
يَجْـَٔرُونَ ﴿٦٤﴾ لَا تَجْـَٔرُواْ ٱلْيَوْمَ ۖ إِنَّكُم مِّنَّا لَا تُنصَرُونَ ﴿٦٥﴾ قَدْ كَانَتْ
ءَايَٰتِى تُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ فَكُنتُمْ عَلَىٰٓ أَعْقَٰبِكُمْ تَنكِصُونَ ﴿٦٦﴾
مُسْتَكْبِرِينَ بِهِۦ سَٰمِرًا تَهْجُرُونَ ﴿٦٧﴾ أَفَلَمْ يَدَّبَّرُواْ ٱلْقَوْلَ أَمْ
جَآءَهُم مَّا لَمْ يَأْتِ ءَابَآءَهُمُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٦٨﴾ أَمْ لَمْ يَعْرِفُواْ رَسُولَهُمْ
فَهُمْ لَهُۥ مُنكِرُونَ ﴿٦٩﴾ أَمْ يَقُولُونَ بِهِۦ جِنَّةٌ ۚ بَلْ جَآءَهُم بِٱلْحَقِّ
وَأَكْثَرُهُمْ لِلْحَقِّ كَٰرِهُونَ ﴿٧٠﴾ وَلَوِ ٱتَّبَعَ ٱلْحَقُّ أَهْوَآءَهُمْ لَفَسَدَتِ
ٱلسَّمَٰوَٰتُ وَٱلْأَرْضُ وَمَن فِيهِنَّ ۚ بَلْ أَتَيْنَٰهُم بِذِكْرِهِمْ فَهُمْ
عَن ذِكْرِهِم مُّعْرِضُونَ ﴿٧١﴾ أَمْ تَسْـَٔلُهُمْ خَرْجًا فَخَرَاجُ رَبِّكَ خَيْرٌ ۖ
وَهُوَ خَيْرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ﴿٧٢﴾ وَإِنَّكَ لَتَدْعُوهُمْ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٧٣﴾
وَإِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِٱلْءَاخِرَةِ عَنِ ٱلصِّرَٰطِ لَنَٰكِبُونَ ﴿٧٤﴾

(60) Kuma waɗanda suke ba da abin da suka bayar (na ayyukan kirki), alhali kuwa zukatansu suna tsorace(1), don kuwa lalle su masu komawa ne zuwa ga Ubangijinsu
(61) Waɗannan su ne suke gaggawa ga ayyukan alheri, suna kuma masu rige-rige gare su
(62) Ba Ma kuwa ɗora wa kowane rai wani abu sai wanda zai iya. Kuma a wurinmu akwai littafi da yake furuci da gaskiya, kuma su ba za a zalunce su ba
(63) A'a, ba haka ba ne, zukatansu dai suna cikin gafala daga wannan (littafi mai furta gaskiya), suna kuma da wasu ayyukan ban da waɗannan waɗanda suke aikatawa
(64) Har yayin da Muka kama mawadatansu da azaba sai ga su suna kururuwa
(65) (Sai a ce da su): "Kada ku yi kururuwa a yau; lalle ku ba za a kare ku ba daga gare Mu
(66) "Haƙiƙa ayoyina sun kasance ana karanta muku su, sai kuka zamanto kuna komawa da baya
(67) "Kuna masu girman kai (na ƙin imani) a wurinsa (Ɗakin Ka'aba), kuna masu hira, kuna ɓata (Alƙur'ani)."
(68) Me ya sa ne ba su yi zuzzurfan tunani ba game da Alƙur'ani, ko kuwa wani abu ne ya zo musu da bai zo wa iyayensu na farko ba?
(69) Ko kuwa ba su san Manzonsu ba ne, don haka ba su tantance da shi ba?
(70) Ko kuwa cewa suke yi ya taɓu? A'a, ya zo musu ne da gaskiya, sai dai yawancinsu masu ƙin gaskiya ne
(71) Da kuma Alƙur'ani ya biye ma son ransu, to da lallai sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu duka sun lalace. A'a, Mun dai zo musu ne da abin alfaharinsu, amma kuma suna masu bijire wa abin alfaharin nasu
(72) Ko kuwa kana neman lada ne a wurinsu, to ladan Ubangijinka shi ya fi alheri; kuma Shi ne Fiyayyen masu arzutawa
(73) Kuma lalle kai tabbas kana kiran su ne zuwa ga hanya madaidaiciya
(74) Lalle kuma waɗanda ba sa yin imani da lahira tabbas su masu bauɗewa ne daga hanya

(1) Watau suna cike da tsoron za a karɓa ko ba za a karɓa ba.




* وَلَوْ رَحِمْنَٰهُمْ وَكَشَفْنَا مَا بِهِم مِّن ضُرٍّ لَّلَجُّوا۟ فِى طُغْيَٰنِهِمْ
يَعْمَهُونَ ﴿٧٥﴾ وَلَقَدْ أَخَذْنَٰهُم بِٱلْعَذَابِ فَمَا ٱسْتَكَانُوا۟ لِرَبِّهِمْ
وَمَا يَتَضَرَّعُونَ ﴿٧٦﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا فَتَحْنَا عَلَيْهِم بَابًا ذَا عَذَابٍ شَدِيدٍ
إِذَا هُمْ فِيهِ مُبْلِسُونَ ﴿٧٧﴾ وَهُوَ ٱلَّذِىٓ أَنشَأَ لَكُمُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ
وَٱلْأَفْـِٔدَةَ ۚ قَلِيلًا مَّا تَشْكُرُونَ ﴿٧٨﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى ذَرَأَكُمْ فِى ٱلْأَرْضِ
وَإِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ﴿٧٩﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى يُحْىِۦ وَيُمِيتُ وَلَهُ ٱخْتِلَٰفُ
ٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿٨٠﴾ بَلْ قَالُوا۟ مِثْلَ مَا قَالَ
ٱلْأَوَّلُونَ ﴿٨١﴾ قَالُوٓا۟ أَءِذَا مِتْنَا وَكُنَّا تُرَابًا وَعِظَٰمًا أَءِنَّا
لَمَبْعُوثُونَ ﴿٨٢﴾ لَقَدْ وُعِدْنَا نَحْنُ وَءَابَآؤُنَا هَٰذَا مِن قَبْلُ
إِنْ هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٨٣﴾ قُل لِّمَنِ ٱلْأَرْضُ وَمَن
فِيهَآ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٨٤﴾ سَيَقُولُونَ لِلَّهِ ۚ قُلْ أَفَلَا
تَذَكَّرُونَ ﴿٨٥﴾ قُلْ مَن رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ ٱلسَّبْعِ وَرَبُّ ٱلْعَرْشِ
ٱلْعَظِيمِ ﴿٨٦﴾ سَيَقُولُونَ لِلَّهِ ۚ قُلْ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿٨٧﴾ قُلْ مَنۢ
بِيَدِهِۦ مَلَكُوتُ كُلِّ شَىْءٍ وَهُوَ يُجِيرُ وَلَا يُجَارُ عَلَيْهِ إِن
كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٨٨﴾ سَيَقُولُونَ لِلَّهِ ۚ قُلْ فَأَنَّىٰ تُسْحَرُونَ ﴿٨٩﴾

(75) Da kuwa Mun ji ƙan su Mun kuma yaye musu cutar da take tare da su (ta fari), to tabbas da sun zarce cikin shisshiginsu suna fagamniya
(76) Kuma haƙiƙa Mun kama su da azaba amma ba su miƙa wuya ga Ubangijinsu ba, ba sa kuma ƙasƙantar da kai
(77) Har dai yayin da Muka buɗe musu ƙofa mai matsananciyar azaba sai ga su cikinta suna masu yanke ƙauna (daga kowace rahama)
(78) Shi ne kuma (Allah) wanda Ya halitta muku ji da gani da kuma zukata. Kaɗan ƙwarai kuke gode wa (masa)
(79) Shi ne kuma wanda Ya halicce ku a bayan ƙasa, kuma zuwa gare Shi za a tattara ku
(80) Kuma Shi ne Yake rayawa Yake kuma kashewa, kuma sassaɓawar dare da rana nasa ne. Me ya sa ba kwa hankalta ne?
(81) A'a, sun dai faɗi irin abin da (mutanen) farko suka faɗa ne
(82) (Wato) sun ce: "Yanzu wai idan mun mutu kuma mun zama turɓaya da ƙasusuwa, anya za a kuwa tashe mu?
(83) "Haƙiƙa mu da iyayenmu an yi mana alƙawarin wannan tun tuni, wannan ba wani abu ba ne in ban da tatsuniyoyin mutan da."
(84) Ka ce (da su): "Kasa da abin da yake cikinta na Wane ne, idan kun kasance kun sani?"
(85) Ai za ka ji sun ce: "Na Allah ne." Ka ce (da su): "To me ya sa ba kwa wa'azantuwa ne?"
(86) Ka ce (da su): "Wane ne Ubangijin sammai bakwai kuma Ubangijin Al'arshi mai girma?"
(87) Ai za su ce: "Na Allah ne." Ka ce (da su): "To me ya sa ba kwa taƙawa?"
(88) Ka ce (da su): "Wane ne mulkin komai yake a hannunsa, kuma Shi ne Yake kariya, (Shi) kuma ba a kare wani daga gare Shi, idan kun kasance kun sani?"
(89) Ai za su ce: "Na Allah ne." Ka ce (da su): "To ta ina ne ake tafiyar muku da hankalinku?"

بَلْ أَتَيْنَٰهُم بِٱلْحَقِّ وَإِنَّهُمْ لَكَٰذِبُونَ ﴿٩٠﴾ مَا ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ مِن
وَلَدٍ وَمَا كَانَ مَعَهُۥ مِنْ إِلَٰهٍ ۚ إِذًا لَّذَهَبَ كُلُّ إِلَٰهٍۭ بِمَا خَلَقَ
وَلَعَلَا بَعْضُهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ ۚ سُبْحَٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يَصِفُونَ ﴿٩١﴾
عَٰلِمِ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ فَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٩٢﴾ قُل رَّبِّ
إِمَّا تُرِيَنِّى مَا يُوعَدُونَ ﴿٩٣﴾ رَبِّ فَلَا تَجْعَلْنِى فِى ٱلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ
﴿٩٤﴾ وَإِنَّا عَلَىٰٓ أَن نُّرِيَكَ مَا نَعِدُهُمْ لَقَٰدِرُونَ ﴿٩٥﴾ ٱدْفَعْ بِٱلَّتِى
هِىَ أَحْسَنُ ٱلسَّيِّئَةَ ۚ نَحْنُ أَعْلَمُ بِمَا يَصِفُونَ ﴿٩٦﴾ وَقُل رَّبِّ
أَعُوذُ بِكَ مِنْ هَمَزَٰتِ ٱلشَّيَٰطِينِ ﴿٩٧﴾ وَأَعُوذُ بِكَ رَبِّ أَن
يَحْضُرُونِ ﴿٩٨﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَ أَحَدَهُمُ ٱلْمَوْتُ قَالَ رَبِّ
ٱرْجِعُونِ ﴿٩٩﴾ لَعَلِّىٓ أَعْمَلُ صَٰلِحًا فِيمَا تَرَكْتُ ۚ كَلَّآ ۚ إِنَّهَا
كَلِمَةٌ هُوَ قَآئِلُهَا ۖ وَمِن وَرَآئِهِم بَرْزَخٌ إِلَىٰ يَوْمِ يُبْعَثُونَ ﴿١٠٠﴾
فَإِذَا نُفِخَ فِى ٱلصُّورِ فَلَآ أَنسَابَ بَيْنَهُمْ يَوْمَئِذٍ وَلَا يَتَسَآءَلُونَ
﴿١٠١﴾ فَمَن ثَقُلَتْ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ﴿١٠٢﴾ وَمَنْ
خَفَّتْ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ فِى جَهَنَّمَ
خَٰلِدُونَ ﴿١٠٣﴾ تَلْفَحُ وُجُوهَهُمُ ٱلنَّارُ وَهُمْ فِيهَا كَٰلِحُونَ ﴿١٠٤﴾

(90) A'a, Mun dai zo musu ne da gaskiya, su kuwa lalle tabbas makaryata ne
(91) Allah bai riki wani da ba, kuma babu wani abin bauta tare da Shi. (Da ko haka ta faru) to da kowanne abin bauta ya kebanta da abin da ya halitta, da kuma wani ya yi rinjaye a kan wani. Allah Ya tsarkaka daga abin da suke sifanta (Shi da shi)
(92) Shi ne Masanin boye da sarari, to Ya daukaka daga abin da suke shirka (da Shi)
(93) Ka ce: "Ubangijina, idan Ka nuna min abin da ake yi musu alkawari da shi (na azaba)

(94) "Ubangijina, kada Ka sanya ni cikin mutane azzalumai."(95)Mu kuma lalle Masu iko ne a kan Mu nuna maka abin da Muke musu alkawari
(96) Ka ingije mummunan abu da wanda ya fi kyau. Mu ne Muka fi sanin abin da suke siffata (ka da shi)
(97) Kuma ka ce: "Ubangijina, ina neman tsarinka daga waswasin shaidanu
(98) "Ina kuma neman tsarinka Ubangijina kar su zo min."(99) Har sai idan da mutuwa ta zo wa dayansu zai ce: "Ubangijina, Ku mai da ni (duniya) mana
(100) "Don in yi aiki na gari game da abin da na bari (a rayuwata)." Ina! Lalle wannan kalma ce da yake fadin ta (da bakinsa). A gabansu kuwa akwai shamaki har zuwa ranar tashinsu
(101) Sannan idan aka busa kaho to fa babu wata dangantaka (mai amfani) a tsakaninsu a wannan ranar, kuma ba za su tambayi juna ba
(102) To wadanda ma'aunansu suka yi nauyi wadannan su ne masu babban rabo
(103) Wadanda kuwa ma'aunansu suka yi sakayau wadannan su ne wadanda suka yi asarar kawunansu, suna masu dawwama a cikin (wutar) Jahannama
(104) (Wutar) tana kona fuskokinsu alhali kuwa suna ciccije hakoransu a cikinta


أَلَمْ تَكُنْ ءَايَٰتِى تُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ فَكُنتُم بِهَا تُكَذِّبُونَ ﴿١٠٥﴾ قَالُوا۟
رَبَّنَا غَلَبَتْ عَلَيْنَا شِقْوَتُنَا وَكُنَّا قَوْمًا ضَآلِّينَ ﴿١٠٦﴾ رَبَّنَآ
أَخْرِجْنَا مِنْهَا فَإِنْ عُدْنَا فَإِنَّا ظَٰلِمُونَ ﴿١٠٧﴾ قَالَ ٱخْسَـُٔوا۟ فِيهَا
وَلَا تُكَلِّمُونِ ﴿١٠٨﴾ إِنَّهُۥ كَانَ فَرِيقٌ مِّنْ عِبَادِى يَقُولُونَ رَبَّنَآ ءَامَنَّا
فَٱغْفِرْ لَنَا وَٱرْحَمْنَا وَأَنتَ خَيْرُ ٱلرَّٰحِمِينَ ﴿١٠٩﴾ فَٱتَّخَذْتُمُوهُمْ
سِخْرِيًّا حَتَّىٰٓ أَنسَوْكُمْ ذِكْرِى وَكُنتُم مِّنْهُمْ تَضْحَكُونَ ﴿١١٠﴾
إِنِّى جَزَيْتُهُمُ ٱلْيَوْمَ بِمَا صَبَرُوٓا۟ أَنَّهُمْ هُمُ ٱلْفَآئِزُونَ ﴿١١١﴾ قَٰلَ
كَمْ لَبِثْتُمْ فِى ٱلْأَرْضِ عَدَدَ سِنِينَ ﴿١١٢﴾ قَالُوا۟ لَبِثْنَا يَوْمًا أَوْ بَعْضَ
يَوْمٍ فَسْـَٔلِ ٱلْعَآدِّينَ ﴿١١٣﴾ قَٰلَ إِن لَّبِثْتُمْ إِلَّا قَلِيلًا ۖ لَّوْ أَنَّكُمْ
كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿١١٤﴾ أَفَحَسِبْتُمْ أَنَّمَا خَلَقْنَٰكُمْ عَبَثًا وَأَنَّكُمْ
إِلَيْنَا لَا تُرْجَعُونَ ﴿١١٥﴾ فَتَعَٰلَى ٱللَّهُ ٱلْمَلِكُ ٱلْحَقُّ ۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا
هُوَ رَبُّ ٱلْعَرْشِ ٱلْكَرِيمِ ﴿١١٦﴾ وَمَن يَدْعُ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا
ءَاخَرَ لَا بُرْهَٰنَ لَهُۥ بِهِۦ فَإِنَّمَا حِسَابُهُۥ عِندَ رَبِّهِۦٓ ۚ إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ
ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿١١٧﴾ وَقُل رَّبِّ ٱغْفِرْ وَٱرْحَمْ وَأَنتَ خَيْرُ ٱلرَّٰحِمِينَ ﴿١١٨﴾
سُورَةُ النُّورِ

(105) Yanzu ayoyina ba su zamanto ana karanta muku su ba, sai ya zamana kuna ƙaryata su?
(106) Suka ce: "Ya Ubangijinmu, tsiyarmu ce ta rinjaye mu, mun kuma zamo mutane ɓatattu
(107) "Ya Ubangijinmu, Ka fitar da mu daga cikinta, to idan muka sake, to lalle mu azzalumai ne."
(108) Ya ce: "Ku yi min shiru, kada kuwa ku ƙara yi min magana a cikinta
(109) "Lalle yadda lamarin yake, wata ƙungiya daga bayina sun kasance suna cewa: "Ya Ubangijinmu, mun yi imani, sai Ka gafarta mana, kuma Ka ji ƙan mu, Kai ne kuwa Fiyayyen masu jin ƙai
(110) "Sai kuka ɗauke su ababen yi wa izgili, har suka mantar da ku ambatona kuka kuma kasance kuna yi musu dariya(111) "Lalle Ni Na saka musu a yau saboda haƙurinsu. Lalle kuma su ne marabauta."
(112) Ya ce: "Zaman shekara nawa kuka yi a bayan ƙasa?"
(113) Suka ce: "Mun zauna ne yini ɗaya ko rabin yini, sai Ka tambayi (mala'iku) masu lissafin (kwanaki)
(114) Ya ce: "Ai ba ku zauna ba sai ɗan lokaci ƙanƙani (dangane da zaman lahira), da a ce kun kasance kun san da haka."
(115) (Allah Ya ce da su): "Ko kuna tsammani ne cewa Mun halicce ku ne ba manufa kuma ku ba za a dawo da ku gare Mu ba?"
(116) To Allah Sarki na gaskiya Ya ɗaukaka; babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, (Shi ne) Ubangijin Al'arshi mai girma
(117) Duk wanda ya bauta wa wani abin bauta tare da Allah ba da wata hujja ba game da (wannan bautar), to sakamakonsa wajen Ubangijinsa kawai yake. Lalle su dai kafirai ba za su rabauta ba
(118) Kuma ka ce: "Ya Ubangijina Ka gafarta (mana) kuma Ka ji ƙan mu, Kai ne kuwa Fiyayyen masu jin ƙai."

Sura Nur

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

سُورَةٌ أَنزَلۡنَٰهَا وَفَرَضۡنَٰهَا وَأَنزَلۡنَا فِيهَآ ءَايَٰتِۭ بَيِّنَٰتٖ لَّعَلَّكُمۡ تَذَكَّرُونَ ١ ٱلزَّانِيَةُ وَٱلزَّانِي فَٱجۡلِدُواْ كُلَّ وَٰحِدٖ مِّنۡهُمَا مِاْئَةَ جَلۡدَةٖۖ وَلَا تَأۡخُذۡكُم بِهِمَا رَأۡفَةٞ فِي دِينِ ٱللَّهِ إِن كُنتُمۡ تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۖ وَلۡيَشۡهَدۡ عَذَابَهُمَا طَآئِفَةٞ مِّنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٢ ٱلزَّانِي لَا يَنكِحُ إِلَّا زَانِيَةً أَوۡ مُشۡرِكَةٗ وَٱلزَّانِيَةُ لَا يَنكِحُهَآ إِلَّا زَانٍ أَوۡ مُشۡرِكٞۚ وَحُرِّمَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٣ وَٱلَّذِينَ يَرۡمُونَ ٱلۡمُحۡصَنَٰتِ ثُمَّ لَمۡ يَأۡتُواْ بِأَرۡبَعَةِ شُهَدَآءَ فَٱجۡلِدُوهُمۡ ثَمَٰنِينَ جَلۡدَةٗ وَلَا تَقۡبَلُواْ لَهُمۡ شَهَٰدَةً أَبَدٗاۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ ٤ إِلَّا ٱلَّذِينَ تَابُواْ مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ وَأَصۡلَحُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٥ وَٱلَّذِينَ يَرۡمُونَ أَزۡوَٰجَهُمۡ وَلَمۡ يَكُن لَّهُمۡ شُهَدَآءُ إِلَّآ أَنفُسُهُمۡ فَشَهَٰدَةُ أَحَدِهِمۡ أَرۡبَعُ شَهَٰدَٰتِۭ بِٱللَّهِ إِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٦ وَٱلۡخَٰمِسَةُ أَنَّ لَعۡنَتَ ٱللَّهِ عَلَيۡهِ إِن كَانَ مِنَ ٱلۡكَٰذِبِينَ ٧ وَيَدۡرَؤُاْ عَنۡهَا ٱلۡعَذَابَ أَن تَشۡهَدَ أَرۡبَعَ شَهَٰدَٰتِۭ بِٱللَّهِ إِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلۡكَٰذِبِينَ ٨ وَٱلۡخَٰمِسَةَ أَنَّ غَضَبَ ٱللَّهِ عَلَيۡهَآ إِن كَانَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٩ وَلَوۡلَا فَضۡلُ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ وَرَحۡمَتُهُۥ وَأَنَّ ٱللَّهَ تَوَّابٌ حَكِيمٌ ١٠

(1) Wannan Sura ce da Muka saukar da ita Muka kuma wajabta (hukunce-hukuncen da suke cikinta), Muka kuma saukar da ayoyi bayyanannu a cikinta don ku wa'azantu
(2) Mazinaciya da mazinaci (idan suka yi zina) sai ku yi wa kowanne ɗaya daga cikinsu bulala ɗari[1], kada kuwa wani tausayi ya kama ku game da (tabbatar da hukuncin) addinin Allah idan kun kasance kuna imani da Allah da ranar lahira; kuma lalle ne wata ƙungiya daga cikin muminai su halarci (wurin) yi musu haddin
(3) Mazinaci ba ya aure sai da karuwa ko mushirika, karuwa kuma ba ta aure sai da mazinaci ko mushiriki. An kuma haramta wannan ga muminai
(4) Waɗanda kuwa suke jifan mata masu kamun kai sannan ba su kawo shaidu huɗu ba, sai ku yi musu bulala tamanin, kuma kada ku karɓi shaidarsu har abada. Waɗannan kuma su ne fasiƙai
(5) Sai dai waɗanda suka tuba bayan wannan suka kuma gyara, to haƙiƙa Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai ne
(6) Waɗanda kuma suke jifan matayensu (da zina) kuma ba su da wasu shaidu sai su kansu, to shaidar ɗayansu ita ce ya rantsuwa da Allah sau huɗu a kan cewa shi lalle yana daga masu gaskiya
(7) (Rantsuwa) ta biyar kuwa kan cewa tsinuwar Allah ta hau kansa in ya kasance daga cikin maƙaryata
(8) Kuma (abin da) zai kawar mata da azabar haddi shi ne ta yi rantsuwa da Allah sau huɗu kan cewa shi lalle yana daga cikin maƙaryata
(9) (Rantsuwa) ta biyar kuwa kan cewa lalle fushin Allah ya hau kanta idan ya kasance daga masu gaskiya
(10) Ba don falalar Allah gare ku ba da rahamarsa, da kuma cewa Allah Mai karɓar tuba ne, Mai hikima (to da ya kunyata maƙaryaci)

(1) Ga waɗanda ba su yi aure ba, bayan an samu shaidun gani da ido maza huɗu; ko sun yi iƙirari; ko ta zo da ciki ba tare da aure ba kuma ba sa-ɗaka ba.

إِنَّ ٱلَّذِينَ جَآءُو بِٱلْإِفْكِ عُصْبَةٌ مِّنكُمْ ۚ لَا تَحْسَبُوهُ شَرًّا لَّكُم ۖ بَلْ
هُوَ خَيْرٌ لَّكُمْ ۚ لِكُلِّ ٱمْرِئٍ مِّنْهُم مَّا ٱكْتَسَبَ مِنَ ٱلْإِثْمِ ۚ وَٱلَّذِى تَوَلَّىٰ
كِبْرَهُۥ مِنْهُمْ لَهُۥ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿١١﴾ لَّوْلَآ إِذْ سَمِعْتُمُوهُ ظَنَّ ٱلْمُؤْمِنُونَ
وَٱلْمُؤْمِنَٰتُ بِأَنفُسِهِمْ خَيْرًا وَقَالُوا۟ هَٰذَآ إِفْكٌ مُّبِينٌ ﴿١٢﴾ لَّوْلَا
جَآءُو عَلَيْهِ بِأَرْبَعَةِ شُهَدَآءَ ۚ فَإِذْ لَمْ يَأْتُوا۟ بِٱلشُّهَدَآءِ فَأُو۟لَٰٓئِكَ
عِندَ ٱللَّهِ هُمُ ٱلْكَٰذِبُونَ ﴿١٣﴾ وَلَوْلَا فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ
فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ لَمَسَّكُمْ فِى مَآ أَفَضْتُمْ فِيهِ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿١٤﴾
إِذْ تَلَقَّوْنَهُۥ بِأَلْسِنَتِكُمْ وَتَقُولُونَ بِأَفْوَٰهِكُم مَّا لَيْسَ لَكُم بِهِۦ عِلْمٌ
وَتَحْسَبُونَهُۥ هَيِّنًا وَهُوَ عِندَ ٱللَّهِ عَظِيمٌ ﴿١٥﴾ وَلَوْلَآ إِذْ سَمِعْتُمُوهُ
قُلْتُم مَّا يَكُونُ لَنَآ أَن نَّتَكَلَّمَ بِهَٰذَا سُبْحَٰنَكَ هَٰذَا بُهْتَٰنٌ عَظِيمٌ
﴿١٦﴾ يَعِظُكُمُ ٱللَّهُ أَن تَعُودُوا۟ لِمِثْلِهِۦٓ أَبَدًا إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٧﴾
وَيُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلْءَايَٰتِ ۚ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿١٨﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ
يُحِبُّونَ أَن تَشِيعَ ٱلْفَٰحِشَةُ فِى ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ
فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ ۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿١٩﴾ وَلَوْلَا
فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ وَأَنَّ ٱللَّهَ رَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿٢٠﴾

(11) Lalle waɗanda suka zo da ƙagaggiyar ƙarya wasu jama'a ne daga cikinku[1]. Kada ku zace shi sharri ne a gare ku; a'a, shi alheri ne a gare ku. Kowanne mutum daga cikinsu yana da sakamakon abin da ya aikata na zunubi. Wanda kuwa ya jiɓinci fara kwaza shi daga cikinsu[2] yana da azaba mai girma

(12) Me ya hana lokacin da kuka ji shi (wato ƙyagen) muminai maza da muminai mata ba su yi wa kawunansu zaton alheri ba suka kuma ce, wannan ai ƙage ne bayyananne?

(13) Me ya hana su kawo shaidu huɗu game da shi (ƙagen)? To tun da yake ba su kawo shaidun ba, to waɗannan a wurin Allah su ne maƙaryata

(14) Ba don kuwa falalar Allah a gare ku da rahamarsa ba a duniya da lahira, to tabbas da azaba mai girma ta shafe ku game da abin da kuka kutsa cikinsa

(15) Yayin da kuke bayeyeniyarsa (ƙagen) da harsunanku, kuke faɗar abin da ba ku sani ba da bakunanku, kuke kuma tsammaninsa abu ne mai sauƙi, alhali kuwa shi mai girma ne a wurin Allah

(16) Me ya hana yayin da kuka ji shi ku ce: "Bai dace da mu mu yi irin wannan magana ba," (kuma ku ce:) "Subhanallahi! Ai wannan ƙage ne babba!"

(17) Allah Yana gargaɗin ku kada ku koma yin irinsa har abada idan kun zamanto muminai


(18) Allah kuma yana bayyana muku ayoyinsa ne, Allah kuwa Masani ne, Mai hikima

(19) Lalle waɗanda suke son yaɗuwar mummunan abu a cikin waɗanda suka yi imani suna da (sakamakon) azaba mai raɗaɗi a duniya da lahira, kuma Allah (Shi) ne Yake sane, ku ba ba ku san komai ba

(20) Ba don kuwa falalar Allah a gare ku da rahamarsa ba, da kuma cewa lalle Allah Mai tausayi ne, Mai rahama (da kun faɗa cikin hallaka)

(1) Daga nan zuwa aya ta 26 suna magana ne a kan ƙazafin zina da munafukai suka yi wa Nana A'isha ( ).

(2) Shi ne shugaban munafukan Madina Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salul.


* يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّبِعُواْ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيۡطَٰنِۚ وَمَن يَتَّبِعۡ
خُطُوَٰتِ ٱلشَّيۡطَٰنِ فَإِنَّهُۥ يَأۡمُرُ بِٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِۚ وَلَوۡلَا
فَضۡلُ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ وَرَحۡمَتُهُۥ مَا زَكَىٰ مِنكُم مِّنۡ أَحَدٍ أَبَدٗا وَلَٰكِنَّ
ٱللَّهَ يُزَكِّي مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ٢١ وَلَا يَأۡتَلِ أُوْلُواْ ٱلۡفَضۡلِ
مِنكُمۡ وَٱلسَّعَةِ أَن يُؤۡتُوٓاْ أُوْلِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينَ وَٱلۡمُهَٰجِرِينَ
فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۖ وَلۡيَعۡفُواْ وَلۡيَصۡفَحُوٓاْۗ أَلَا تُحِبُّونَ أَن يَغۡفِرَ ٱللَّهُ
لَكُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٌ ٢٢ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَرۡمُونَ ٱلۡمُحۡصَنَٰتِ
ٱلۡغَٰفِلَٰتِ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ لُعِنُواْ فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِ وَلَهُمۡ عَذَابٌ
عَظِيمٞ ٢٣ يَوۡمَ تَشۡهَدُ عَلَيۡهِمۡ أَلۡسِنَتُهُمۡ وَأَيۡدِيهِمۡ وَأَرۡجُلُهُم بِمَا
كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٢٤ يَوۡمَئِذٖ يُوَفِّيهِمُ ٱللَّهُ دِينَهُمُ ٱلۡحَقَّ وَيَعۡلَمُونَ أَنَّ
ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡحَقُّ ٱلۡمُبِينُ ٢٥ ٱلۡخَبِيثَٰتُ لِلۡخَبِيثِينَ وَٱلۡخَبِيثُونَ
لِلۡخَبِيثَٰتِۖ وَٱلطَّيِّبَٰتُ لِلطَّيِّبِينَ وَٱلطَّيِّبُونَ لِلطَّيِّبَٰتِۚ
أُوْلَٰٓئِكَ مُبَرَّءُونَ مِمَّا يَقُولُونَۖ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ٢٦ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَدۡخُلُواْ بُيُوتًا غَيۡرَ بُيُوتِكُمۡ حَتَّىٰ تَسۡتَأۡنِسُواْ
وَتُسَلِّمُواْ عَلَىٰٓ أَهۡلِهَاۚ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَذَكَّرُونَ ٢٧

(21) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku bi hanyoyin Shaiɗan, wanda kuwa duk ya bi hanyoyin Shaiɗan, to lalle shi (Shaiɗan) umarni yake yi da aikata alfasha da abin ƙyama. Ba don kuma falalar Allah a gare ku da rahamarsa ba, da babu ɗaya daga cikinku da zai tsarkaka har abada, sai dai kuma Allah (Shi) Yake tsarkake wanda Ya ga dama, Allah kuwa Mai ji ne, Masani

(22) Kuma kada masu hali da wadata daga cikinku su rantse a kan ƙin ba da (abin hannunsu) ga makusanta da miskinai da masu hijira saboda Allah. Su kuma yi afuwa su yafe. Shin ku ba kwa so ne Allah Ya gafarta muku? Allah kuwa Mai gafara ne, Mai jin ƙai[1]

(23) Lalle waɗanda suke jifan kamammun mata waɗanda ba su san me yake faruwa ba, muminai, (suke jifan su da zina), to an la'ance su duniya da lahira, kuma suna da (sakamakon) azaba mai girma

(24) A ranar da harsunansu da hannayensu da kuma ƙafafunsu za su ba da shaida a kansu game da abin da suka kasance suna aikatawa

(25) A wannan ranar Allah zai ba su cikakken sakamakonsu na gaskiya kuma za su san cewa lalle Allah Shi ne gaskiya bayyananniya

(26) Miyagun mata da miyagun maganganu sun dace da miyagun maza. Kuma miyagun maza da miyagun maganganu sun dace ne da miyagun mata. Tsarkakan mata da tsarkakan maganganu sun dace da tsarkakan maza. Kuma tsarkakan maza da tsakakan maganganu sun dace da tsarkakan mata. Su waɗannan (tsarkaka) kuwa wankakakku ne daga abin da suke faɗa (na ƙage a kansu), suna da (sakamakon) gafara da arziki mai girma

(27) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku shiga gidajen da ba naku ba har sai kun nemi izini, kuma kun yi sallama ga masu su. Wannan kuwa shi ya fi alheri a gare ku don ku wa'azantu

(1) Ayar tana magana ne a kan Abubakar ( ) lokacin da ya yi rantsuwa ba zai ci gaba da taimaka wa ɗan innarsa Misɗahu ɗan Usasa ba domin ya zama cikin masu kwaza ƙagen da aka yi wa Nana A'isha (RAH)..

فَإِن لَّمْ تَجِدُوا۟ فِيهَآ أَحَدًا فَلَا تَدْخُلُوهَا حَتَّىٰ يُؤْذَنَ لَكُمْ ۖ
وَإِن قِيلَ لَكُمُ ٱرْجِعُوا۟ فَٱرْجِعُوا۟ ۖ هُوَ أَزْكَىٰ لَكُمْ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا
تَعْمَلُونَ عَلِيمٌ ﴿٢٨﴾ لَّيْسَ عَلَيْكُمْ جُنَاحٌ أَن تَدْخُلُوا۟ بُيُوتًا
غَيْرَ مَسْكُونَةٍ فِيهَا مَتَٰعٌ لَّكُمْ ۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ مَا تُبْدُونَ وَمَا
تَكْتُمُونَ ﴿٢٩﴾ قُل لِّلْمُؤْمِنِينَ يَغُضُّوا۟ مِنْ أَبْصَٰرِهِمْ وَيَحْفَظُوا۟
فُرُوجَهُمْ ۚ ذَٰلِكَ أَزْكَىٰ لَهُمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرٌۢ بِمَا يَصْنَعُونَ ﴿٣٠﴾
وَقُل لِّلْمُؤْمِنَٰتِ يَغْضُضْنَ مِنْ أَبْصَٰرِهِنَّ وَيَحْفَظْنَ
فُرُوجَهُنَّ وَلَا يُبْدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا مَا ظَهَرَ مِنْهَا ۖ وَلْيَضْرِبْنَ
بِخُمُرِهِنَّ عَلَىٰ جُيُوبِهِنَّ ۖ وَلَا يُبْدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا لِبُعُولَتِهِنَّ
أَوْ ءَابَآئِهِنَّ أَوْ ءَابَآءِ بُعُولَتِهِنَّ أَوْ أَبْنَآئِهِنَّ أَوْ أَبْنَآءِ بُعُولَتِهِنَّ
أَوْ إِخْوَٰنِهِنَّ أَوْ بَنِىٓ إِخْوَٰنِهِنَّ أَوْ بَنِىٓ أَخَوَٰتِهِنَّ أَوْ نِسَآئِهِنَّ
أَوْ مَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُهُنَّ أَوِ ٱلتَّٰبِعِينَ غَيْرِ أُو۟لِى ٱلْإِرْبَةِ مِنَ
ٱلرِّجَالِ أَوِ ٱلطِّفْلِ ٱلَّذِينَ لَمْ يَظْهَرُوا۟ عَلَىٰ عَوْرَٰتِ ٱلنِّسَآءِ ۖ
وَلَا يَضْرِبْنَ بِأَرْجُلِهِنَّ لِيُعْلَمَ مَا يُخْفِينَ مِن زِينَتِهِنَّ ۚ وَتُوبُوٓا۟
إِلَى ٱللَّهِ جَمِيعًا أَيُّهَ ٱلْمُؤْمِنُونَ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿٣١﴾

(28) To idan ba ku sami kowa a cikinsu ba to kada ku shige su har sai an yi muku izini; idan kuwa aka ce da ku ku koma sai ku koma; wannan shi ya fi tsarki a gare ku. Allah kuwa Masanin abin da kuke aikatawa ne

(29) Babu wani laifi a kanku ku shiga gidaje waɗanda ba wani zaune a cikinsu, kuma akwai kayanku a cikinsu[1], kuma Allah Yana sane da abin da kuke bayyanawa da abin da kuke ɓoyewa

(30) Ka ce da muminai maza su kame idanuwansu[2] kuma su kiyaye farjinsu. Wannan shi ya fi tsarki a gare su. Lalle Allah Masanin abin da suke aikatawa ne

(31) Kuma ka ce da muminai mata su kame idanuwansu[3] kuma su kiyaye farjinsu, kada kuma su fito da adonsu sai dai abin da ya bayyana daga gare shi[4]; kuma su sanya lullubinsu a kan wuyan rigunansu[5]; kada kuma su fitar da adonsu sai ga mazajensu ko iyayensu ko iyayen mazajensu ko 'ya'yansu ko 'ya'yayen mazajensu ko 'yan'uwansu maza ko kuma 'ya'yan 'yan'uwansu maza ko 'ya'yan 'yan'uwansu mata ko kuma mata 'yan'uwansu ko kuma bayinsu ko kuma mazaje masu bin su (don neman abinci) ba kuma masu buƙatar mata ba[6], ko kuma ƙananan yara waɗanda ba su san sha'awar al'aurar mata ba; kada kuma su buga ƙafafuwansu don a gane abin da suka ɓoye na adon ƙafafunsu (watau mundaye). Kuma ku tuba ga Allah gaba ɗayanku ya ku waɗannan muminai don ku rabauta

(1) Watau wuraren da aka tanada domin amfanin kowa da kowa, kamar ɗakunan karatu ko shaguna a kasuwanni.

(2) Watau su kawar da idanuwansu daga kallon matan da bai halatta su kalle su ba, hakanan da kallon al'aurarsu.

(3) Watau su kawar da idanuwansu daga kallon abin da bai halatta su kalla ba.

(4) Watau su kawar da idanuwansu daga kallon abin da bai halatta su kalla ba.

(5) Watau su kawar da idanuwansu daga kallon abin da bai halatta su kalla ba.

(6) Watau su kawar da idanuwansu daga kallon abin da bai halatta su kalla ba.

وَأَنكِحُوا۟ ٱلْأَيَـٰمَىٰ مِنكُمْ وَٱلصَّـٰلِحِينَ مِنْ عِبَادِكُمْ وَإِمَآئِكُمْ ۚ إِن
يَكُونُوا۟ فُقَرَآءَ يُغْنِهِمُ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ ۗ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ﴿٣٢﴾
وَلْيَسْتَعْفِفِ ٱلَّذِينَ لَا يَجِدُونَ نِكَاحًا حَتَّىٰ يُغْنِيَهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ ۗ
وَٱلَّذِينَ يَبْتَغُونَ ٱلْكِتَـٰبَ مِمَّا مَلَكَتْ أَيْمَـٰنُكُمْ فَكَاتِبُوهُمْ إِنْ
عَلِمْتُمْ فِيهِمْ خَيْرًا ۖ وَءَاتُوهُم مِّن مَّالِ ٱللَّهِ ٱلَّذِىٓ ءَاتَىٰكُمْ ۚ وَلَا تُكْرِهُوا۟
فَتَيَـٰتِكُمْ عَلَى ٱلْبِغَآءِ إِنْ أَرَدْنَ تَحَصُّنًا لِّتَبْتَغُوا۟ عَرَضَ ٱلْحَيَوٰةِ
ٱلدُّنْيَا ۚ وَمَن يُكْرِههُّنَّ فَإِنَّ ٱللَّهَ مِنۢ بَعْدِ إِكْرَٰهِهِنَّ غَفُورٌ رَّحِيمٌ
﴿٣٣﴾ وَلَقَدْ أَنزَلْنَآ إِلَيْكُمْ ءَايَـٰتٍ مُّبَيِّنَـٰتٍ وَمَثَلًا مِّنَ ٱلَّذِينَ خَلَوْا۟
مِن قَبْلِكُمْ وَمَوْعِظَةً لِّلْمُتَّقِينَ ﴿٣٤﴾ ۞ ٱللَّهُ نُورُ ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ
مَثَلُ نُورِهِۦ كَمِشْكَوٰةٍ فِيهَا مِصْبَاحٌ ۖ ٱلْمِصْبَاحُ فِى زُجَاجَةٍ ۖ
ٱلزُّجَاجَةُ كَأَنَّهَا كَوْكَبٌ دُرِّىٌّ يُوقَدُ مِن شَجَرَةٍ مُّبَـٰرَكَةٍ زَيْتُونَةٍ
لَّا شَرْقِيَّةٍ وَلَا غَرْبِيَّةٍ يَكَادُ زَيْتُهَا يُضِىٓءُ وَلَوْ لَمْ تَمْسَسْهُ نَارٌ ۚ
نُّورٌ عَلَىٰ نُورٍ ۗ يَهْدِى ٱللَّهُ لِنُورِهِۦ مَن يَشَآءُ ۚ وَيَضْرِبُ ٱللَّهُ ٱلْأَمْثَالَ
لِلنَّاسِ ۗ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿٣٥﴾ فِى بُيُوتٍ أَذِنَ ٱللَّهُ أَن تُرْفَعَ
وَيُذْكَرَ فِيهَا ٱسْمُهُۥ يُسَبِّحُ لَهُۥ فِيهَا بِٱلْغُدُوِّ وَٱلْـَٔاصَالِ ﴿٣٦﴾

(32) Kuma ku aurar da marasa aure daga cikinku da kuma na gari daga bayinku da kuyanginku. Idan sun zamanto matalauta to Allah zai wadata su daga falalarsa. Allah kuwa Mai yalwa ne, Masani

(33) Waɗanda kuma ba su sami wadatar yin aure ba su kame kansu har Allah Ya wadata su daga falalarsa. Waɗanda kuwa suke neman fansar kansu daga bayinku[1], sai ku ba su damar fansar kansu, idan kun san suna da halin iya biya; kuma ku ba su wani abu daga dukiyar Allah da Ya ba ku. Kada kuma ku tilasta wa kuyanginku ‘yan mata a kan yin zina idan sun nemi kame kai, don ku nemi amfanin rayuwar duniya. Wanda duk kuwa ya tilasta su, to lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai bayan tilastawar da aka yi musu

(34) Haƙiƙa kuma Mun saukar muku da ayoyi mabayyana da kuma izina daga waɗanda suka wuce gabaninku, kuma da gargaɗi ga masu taƙawa

(35) Allah ne hasken sammai da ƙasa[2]. Misalin haskensa tamkar alkuki ne da fitila take a cikinsa; fitilar kuma tana cikin ƙarau; ƙaran kuma tamkar tauraro ne na lu’ulu’u, ana kunna ta da man bishiya mai albarka ta zaitun, ita ba daga mahudar rana take ba kuma ba daga mafaɗarta ba, kuma manta kamar zai kama da kansa ko da wuta ba ta taɓa shi ba. Haske kan haske. Allah Yana shiryar da wanda Ya ga dama zuwa ga haskensa. Kuma Allah yana buga misalai ne ga mutane. Allah kuwa Masanin komai ne

(36) (Hasken) yana cikin wasu ɗakuna (watau masallatai) waɗanda Allah Ya yi umarni a ɗaukaka, a kuma ambaci sunansa a cikinsu. (Wasu mazaje) suna tasbihi gare Shi a cikinsu safe da yamma

(1) Watau ta hanyar biyan wani kuɗi da za a yanka musu idan sun biya sun zama ‘yantattun ‘ya’ya.

(2) Kuma shi ne mai haskaka zukatan muminai mai shiryar da su.

رِجَالٌ لَّا تُلْهِيهِمْ تِجَارَةٌ وَلَا بَيْعٌ عَن ذِكْرِ اللَّهِ وَإِقَامِ الصَّلَاةِ
وَإِيتَاءِ الزَّكَاةِ يَخَافُونَ يَوْمًا تَتَقَلَّبُ فِيهِ الْقُلُوبُ وَالْأَبْصَارُ ﴿٣٧﴾
لِيَجْزِيَهُمُ اللَّهُ أَحْسَنَ مَا عَمِلُوا وَيَزِيدَهُم مِّن فَضْلِهِ ۗ وَاللَّهُ
يَرْزُقُ مَن يَشَاءُ بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴿٣٨﴾ وَالَّذِينَ كَفَرُوا أَعْمَالُهُمْ كَسَرَابٍ
بِقِيعَةٍ يَحْسَبُهُ الظَّمْآنُ مَاءً حَتَّىٰ إِذَا جَاءَهُ لَمْ يَجِدْهُ شَيْئًا
وَوَجَدَ اللَّهَ عِندَهُ فَوَفَّاهُ حِسَابَهُ ۗ وَاللَّهُ سَرِيعُ الْحِسَابِ ﴿٣٩﴾
أَوْ كَظُلُمَاتٍ فِي بَحْرٍ لُّجِّيٍّ يَغْشَاهُ مَوْجٌ مِّن فَوْقِهِ مَوْجٌ مِّن فَوْقِهِ
سَحَابٌ ظُلُمَاتٌ بَعْضُهَا فَوْقَ بَعْضٍ إِذَا أَخْرَجَ يَدَهُ لَمْ يَكَدْ
يَرَاهَا ۗ وَمَن لَّمْ يَجْعَلِ اللَّهُ لَهُ نُورًا فَمَا لَهُ مِن نُّورٍ ﴿٤٠﴾ أَلَمْ تَرَ أَنَّ
اللَّهَ يُسَبِّحُ لَهُ مَن فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَالطَّيْرُ صَافَّاتٍ ۖ كُلٌّ
قَدْ عَلِمَ صَلَاتَهُ وَتَسْبِيحَهُ ۗ وَاللَّهُ عَلِيمٌ بِمَا يَفْعَلُونَ ﴿٤١﴾ وَلِلَّهِ مُلْكُ
السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ ۖ وَإِلَى اللَّهِ الْمَصِيرُ ﴿٤٢﴾ أَلَمْ تَرَ أَنَّ اللَّهَ يُزْجِي
سَحَابًا ثُمَّ يُؤَلِّفُ بَيْنَهُ ثُمَّ يَجْعَلُهُ رُكَامًا فَتَرَى الْوَدْقَ يَخْرُجُ مِنْ
خِلَالِهِ وَيُنَزِّلُ مِنَ السَّمَاءِ مِن جِبَالٍ فِيهَا مِن بَرَدٍ فَيُصِيبُ بِهِ مَن يَشَاءُ
وَيَصْرِفُهُ عَن مَّن يَشَاءُ ۖ يَكَادُ سَنَا بَرْقِهِ يَذْهَبُ بِالْأَبْصَارِ ﴿٤٣﴾

(37) Wasu mazaje ne waɗanda kasuwanci da saye da sayarwa ba ya shagaltar da su daga ambaton Allah da kuma tsai da salla da ba da zakka, suna jin tsoron ranar da zukata da idanuwa suke raurawa

(38) (Suna haka ne) don Allah Ya saka musu da mafi kyan abin da suka aikata, kuma Ya ƙara musu daga falalarsa. Allah kuwa Yana arzuta wanda Ya ga dama ba da iyaka ba

(39) Waɗanda kuwa suka kafirta ayyukansu kamar kawalwalniya ne a wani faƙo wanda mai jin tsananin ƙishirwa yake zaton ruwa ne, har lokacin da ya zo gare ta ba zai samu komai ba sai ya sami Allah a wurinsa, sai Ya cika masa hisabinsa. Allah kuwa Mai saurin hisabi ne

(40) Ko kuma kamar duffai a cikin kogi mai zurfi da raƙumin ruwa ya lulluɓe shi, daga samansa kuma akwai wani raƙumin ruwan, daga samansa (kuma) akwai wani hadari. Duffai wasu a kan wasu; idan ya fito da hannunsa ba zai iya ganin sa ba. Wanda kuma Allah bai sanya wa haske ba, to ba shi da wani haske

(41) Ba ka gani cewa Allah duk abin da yake sammai da ƙasa yana tasbihi ne gare Shi, haka tsuntsaye kuma sun buɗe fukafukansu sun yi sahu, kowanne ɗayansu ya san sallarsa da tasbihinsa? Allah kuwa Masanin abin da suke aikatawa ne

(42) Kuma mulkin sammai da ƙasa na Allah ne; makoma kuma zuwa ga Allah take

(43) Shin ba ka gani cewa Allah Yana kora gizagizai sannan Ya harhaɗa tsakaninsu sannan Ya mai da su masu hawan juna, sai ka ga ruwan sama yana fitowa ta tsakankaninsa, kuma Yana saukar da wasu kasake (na gizagizai) daga sama waɗanda a cikinsu akwai ƙanƙara, sai Ya sami wanda Ya ga dama da ita (ƙanƙarar) Ya kuma kautar da ita daga wanda Ya ga dama. Hasken walƙiyarsa yana kusa da ya fauce idanu

يُقَلِّبُ ٱللَّهُ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبۡرَةٗ لِّأُوْلِي ٱلۡأَبۡصَٰرِ ﴿٤٤﴾
وَٱللَّهُ خَلَقَ كُلَّ دَآبَّةٖ مِّن مَّآءٖۖ فَمِنۡهُم مَّن يَمۡشِي عَلَىٰ بَطۡنِهِۦ وَمِنۡهُم مَّن
يَمۡشِي عَلَىٰ رِجۡلَيۡنِ وَمِنۡهُم مَّن يَمۡشِي عَلَىٰٓ أَرۡبَعٖۚ يَخۡلُقُ ٱللَّهُ مَا يَشَآءُۚ
إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ﴿٤٥﴾ لَّقَدۡ أَنزَلۡنَآ ءَايَٰتٖ مُّبَيِّنَٰتٖۚ
وَٱللَّهُ يَهۡدِي مَن يَشَآءُ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ﴿٤٦﴾ وَيَقُولُونَ
ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَبِٱلرَّسُولِ وَأَطَعۡنَا ثُمَّ يَتَوَلَّىٰ فَرِيقٞ مِّنۡهُم مِّنۢ بَعۡدِ
ذَٰلِكَۚ وَمَآ أُوْلَٰٓئِكَ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿٤٧﴾ وَإِذَا دُعُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ
لِيَحۡكُمَ بَيۡنَهُمۡ إِذَا فَرِيقٞ مِّنۡهُم مُّعۡرِضُونَ ﴿٤٨﴾ وَإِن يَكُن لَّهُمُ ٱلۡحَقُّ
يَأۡتُوٓاْ إِلَيۡهِ مُذۡعِنِينَ ﴿٤٩﴾ أَفِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ أَمِ ٱرۡتَابُوٓاْ أَمۡ يَخَافُونَ
أَن يَحِيفَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡ وَرَسُولُهُۥۚ بَلۡ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٥٠﴾ إِنَّمَا
كَانَ قَوۡلَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ إِذَا دُعُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ لِيَحۡكُمَ بَيۡنَهُمۡ أَن
يَقُولُواْ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَاۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ﴿٥١﴾ وَمَن
يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَخۡشَ ٱللَّهَ وَيَتَّقۡهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَآئِزُونَ
﴿٥٢﴾ ۞ وَأَقۡسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهۡدَ أَيۡمَٰنِهِمۡ لَئِنۡ أَمَرۡتَهُمۡ لَيَخۡرُجُنَّۖ قُل
لَّا تُقۡسِمُواْۖ طَاعَةٞ مَّعۡرُوفَةٌۚ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ﴿٥٣﴾

(44) Allah Yana jujjuya dare da yini. Lalle game da wannan tabbas akwai izina ga ma'abota hankula

(45) Kuma Allah Ya halicci kowace dabba daga ruwa; sannan daga cikinsu akwai waɗanda suke jan ciki, kuma daga cikinsu akwai waɗanda suke tafiya a kan ƙafa biyu, akwai kuma waɗanda suke tafiya a kan ƙafa huɗu. Allah Yana halittar abin da Ya ga dama. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai

(46) Haƙiƙa Mun saukar da ayoyi masu bayyana komai da komai. Allah kuma Yana shiryar da wanda Ya ga dama zuwa ga tafarki madaidaici

(47) Kuma suna cewa: "Mun yi imani da Allah da kuma Manzo kuma mun bi," sannan wata ƙungiya daga cikinsu takan ba da baya bayan wancan (imanin). Waɗannan kuwa ba muminai ba ne

(48) Idan kuwa aka yi kiran su zuwa ga Allah da Manzonsa don ya yi hukunci a tsakaninsu sai ka ga wata ƙungiya daga cikinsu suna bijirewa

(49) Idan kuwa su ne masu gaskiya sai su zo wurinsa suna masu miƙa wuya

(50) Shin cuta ce a cikin zukatansu, ko kuwa suna tababa ne, ko kuma suna tsoron Allah da Manzonsa su zalunce su ne? A'a, waɗannan su ne azzalumai

(51) Muminai ba su da wata magana idan aka kira su zuwa ga Allah da Manzonsa don ya yi hukunci a tsakaninsu sai faɗar: "Mun ji kuma mun bi." Waɗannan kuwa su ne masu babban rabo

(52) Duk kuwa wanda ya bi Allah da Manzonsa kuma yake tsoron Allah kuma yake kiyaye dokokinsa, to waɗannan su ne masu rabauta

(53) Suka kuma rantse da Allah iya iyawarsu cewa lalle idan ka umarce su (da fita) tabbas za su fita. Ka ce (da su): "Ku daina rantse-rantse; biyayya (taku ta ƙarya) sananniya ce. Lalle Allah Masanin abin da kuke aikatawa ne."

قُلْ أَطِيعُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُوا۟ ٱلرَّسُولَ ۖ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَإِنَّمَا عَلَيْهِ مَا حُمِّلَ
وَعَلَيْكُم مَّا حُمِّلْتُمْ ۖ وَإِن تُطِيعُوهُ تَهْتَدُوا۟ ۚ وَمَا عَلَى ٱلرَّسُولِ
إِلَّا ٱلْبَلَٰغُ ٱلْمُبِينُ ﴿٥٤﴾ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مِنكُمْ وَعَمِلُوا۟
ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَيَسْتَخْلِفَنَّهُمْ فِى ٱلْأَرْضِ كَمَا ٱسْتَخْلَفَ
ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ وَلَيُمَكِّنَنَّ لَهُمْ دِينَهُمُ ٱلَّذِى ٱرْتَضَىٰ
لَهُمْ وَلَيُبَدِّلَنَّهُم مِّنۢ بَعْدِ خَوْفِهِمْ أَمْنًا ۚ يَعْبُدُونَنِى لَا يُشْرِكُونَ
بِى شَيْـًٔا ۚ وَمَن كَفَرَ بَعْدَ ذَٰلِكَ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْفَٰسِقُونَ ﴿٥٥﴾
وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَطِيعُوا۟ ٱلرَّسُولَ لَعَلَّكُمْ
تُرْحَمُونَ ﴿٥٦﴾ لَا تَحْسَبَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مُعْجِزِينَ فِى ٱلْأَرْضِ ۚ
وَمَأْوَىٰهُمُ ٱلنَّارُ ۖ وَلَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ﴿٥٧﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟
لِيَسْتَـْٔذِنكُمُ ٱلَّذِينَ مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُمْ وَٱلَّذِينَ لَمْ يَبْلُغُوا۟ ٱلْحُلُمَ مِنكُمْ
ثَلَٰثَ مَرَّٰتٍ ۚ مِّن قَبْلِ صَلَوٰةِ ٱلْفَجْرِ وَحِينَ تَضَعُونَ ثِيَابَكُم مِّنَ
ٱلظَّهِيرَةِ وَمِنۢ بَعْدِ صَلَوٰةِ ٱلْعِشَآءِ ۚ ثَلَٰثُ عَوْرَٰتٍ لَّكُمْ ۚ لَيْسَ عَلَيْكُمْ
وَلَا عَلَيْهِمْ جُنَاحٌۢ بَعْدَهُنَّ ۚ طَوَّٰفُونَ عَلَيْكُم بَعْضُكُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ ۚ
كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلْـَٔايَٰتِ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿٥٨﴾

(54) Ka ce (da su): "Ku bi Allah kuma ku bi Manzo; sannan idan kuka ba da baya, to lalle nauyin abin da aka ɗora masa ne kawai a kansa; kuma nauyin da aka ɗora muku yana kanku, idan kuwa kuka bi shi za ku shiriya. Ba kuwa abin da yake kan Manzo sai isar da aike mabayyani

(55) Allah kuwa Ya yi wa waɗanda suka yi imani daga cikinku suka kuma yi aiki na gari alƙawarin lalle zai sanya su halifofi a bayan ƙasa kamar yadda Ya sanya waɗanda suke gabaninsu halifofi, kuma lalle zai tabbatar musu da addininsu wanda Ya yardar musu, tabbas kuma zai dawo musu da zaman lafiya bayan zamantowarsu cikin tsoro. Su bauta mini, ba sa yin shirkar komai da Ni. Wanda kuwa ya kafirta bayan wannan, to waɗannan su ne fasiƙai

(56) Kuma ku tsai da salla ku kuma ba da zakka kuma ku bi Manzo don a ji ƙan ku

(57) Kada kuma ka tsammaci waɗanda suka kafirta za su gagara a bayan ƙasa, kuma makomarsu wuta ce; makoma kuwa ta munana

(58) Ya ku waɗanda suka yi imani, bayinku da kuma waɗanda ba su isa mafarki ba a cikinku (watau waɗanda ba su balaga ba) su nemi izininku sau uku. Kafin sallar Asuba da sanda kuke tuɓe tufafinku a lokacin garjin rana da kuma bayan sallar Lisha. Lokatai ne guda uku na tsiraicinku[1]. Babu laifi a kanku ko a kansu bayansu (waɗannan lokatai). Masu shige da fice ne a gare ku sashinku bisa sashi. Kamar haka ne Allah Yake bayyana muku ayoyi. Allah kuma Masani ne, Mai hikima

(1) Watau lokacin da suke sanya tufafin barci ko na shan iska a gida.

وَإِذَا بَلَغَ ٱلْأَطْفَٰلُ مِنكُمُ ٱلْحُلُمَ فَلْيَسْتَـْٔذِنُوا۟ كَمَا
ٱسْتَـْٔذَنَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ ۚ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمْ
ءَايَٰتِهِۦ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿٥٩﴾ وَٱلْقَوَٰعِدُ مِنَ ٱلنِّسَآءِ
ٱلَّٰتِى لَا يَرْجُونَ نِكَاحًا فَلَيْسَ عَلَيْهِنَّ جُنَاحٌ أَن يَضَعْنَ
ثِيَابَهُنَّ غَيْرَ مُتَبَرِّجَٰتٍۭ بِزِينَةٍ ۖ وَأَن يَسْتَعْفِفْنَ خَيْرٌ
لَّهُنَّ ۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٦٠﴾ لَّيْسَ عَلَى ٱلْأَعْمَىٰ حَرَجٌ وَلَا
عَلَى ٱلْأَعْرَجِ حَرَجٌ وَلَا عَلَى ٱلْمَرِيضِ حَرَجٌ وَلَا عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمْ
أَن تَأْكُلُوا۟ مِنۢ بُيُوتِكُمْ أَوْ بُيُوتِ ءَابَآئِكُمْ أَوْ بُيُوتِ
أُمَّهَٰتِكُمْ أَوْ بُيُوتِ إِخْوَٰنِكُمْ أَوْ بُيُوتِ أَخَوَٰتِكُمْ
أَوْ بُيُوتِ أَعْمَٰمِكُمْ أَوْ بُيُوتِ عَمَّٰتِكُمْ أَوْ بُيُوتِ
أَخْوَٰلِكُمْ أَوْ بُيُوتِ خَٰلَٰتِكُمْ أَوْ مَا مَلَكْتُم
مَّفَاتِحَهُۥٓ أَوْ صَدِيقِكُمْ ۚ لَيْسَ عَلَيْكُمْ جُنَاحٌ أَن
تَأْكُلُوا۟ جَمِيعًا أَوْ أَشْتَاتًا ۚ فَإِذَا دَخَلْتُم بُيُوتًا فَسَلِّمُوا۟
عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمْ تَحِيَّةً مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ مُبَٰرَكَةً طَيِّبَةً ۚ كَذَٰلِكَ
يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلْءَايَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿٦١﴾

(59) Idan kuma yara daga cikinku suka isa mafarki (watau suka balaga) sai su nemi izini kamar yadda waɗanda suke gabaninsu suka rika neman izini. Kamar haka Allah Yake bayyana muku ayoyinsa. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima

(60) Tsofaffin mata kuwa waɗanda ba sa tsammanin yin aure to babu laifi a kansu su sauke lullubinsu, amma ba masu fitar da adonsu ba; amma kuma su yi lullubi shi ya fi zama alheri a gare su. Allah kuwa Mai ji ne, Masani

(61) Babu wani laifi a kan makaho, babu kuma wani laifi a kan gurgu, kuma babu wani laifi a kan marar lafiya ko kuma a kanku, kan ku ci a gidajenku ko a gidajen iyayenku maza ko a gidajen iyayenku mata ko a gidajen 'yan'uwanku maza ko a gidajen 'yan'uwanku mata ko a gidajen baffanninku ko a gidajen gwaggwanninku ko kuma a gidajen kawunnanku ko kuma a gidajen yagwalgwalanku, ko kuma abin da kuka mallaki mabuɗansa, ko kuma na abokinku. Babu wani laifi a kanku ku ci tare ko kuma daban-daban, sannan idan za ku shiga gidaje sai ku yi wa junanku sallama, (wannan) gaisuwa ce daga wurin Allah mai albarka tsattsarka. Kamar haka Allah Yake bayyana muku ayoyi don ku hankalta

إِنَّمَا ٱلْمُؤْمِنُونَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَإِذَا كَانُوا۟ مَعَهُۥ
عَلَىٰٓ أَمْرٍ جَامِعٍ لَّمْ يَذْهَبُوا۟ حَتَّىٰ يَسْتَـْٔذِنُوهُ ۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَسْتَـْٔذِنُونَكَ
أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ يُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ۚ فَإِذَا ٱسْتَـْٔذَنُوكَ
لِبَعْضِ شَأْنِهِمْ فَأْذَن لِّمَن شِئْتَ مِنْهُمْ وَٱسْتَغْفِرْ لَهُمُ
ٱللَّهَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٦٢﴾ لَّا تَجْعَلُوا۟ دُعَآءَ ٱلرَّسُولِ
بَيْنَكُمْ كَدُعَآءِ بَعْضِكُم بَعْضًا ۚ قَدْ يَعْلَمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ
يَتَسَلَّلُونَ مِنكُمْ لِوَاذًا ۚ فَلْيَحْذَرِ ٱلَّذِينَ يُخَالِفُونَ عَنْ
أَمْرِهِۦٓ أَن تُصِيبَهُمْ فِتْنَةٌ أَوْ يُصِيبَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٦٣﴾ أَلَآ إِنَّ
لِلَّهِ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ قَدْ يَعْلَمُ مَآ أَنتُمْ عَلَيْهِ وَيَوْمَ
يُرْجَعُونَ إِلَيْهِ فَيُنَبِّئُهُم بِمَا عَمِلُوا۟ ۗ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿٦٤﴾

سُورَةُ الْفُرْقَانِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

تَبَارَكَ ٱلَّذِى نَزَّلَ ٱلْفُرْقَانَ عَلَىٰ عَبْدِهِۦ لِيَكُونَ لِلْعَٰلَمِينَ نَذِيرًا
﴿١﴾ ٱلَّذِى لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَلَمْ يَتَّخِذْ وَلَدًا وَلَمْ يَكُن
لَّهُۥ شَرِيكٌ فِى ٱلْمُلْكِ وَخَلَقَ كُلَّ شَىْءٍ فَقَدَّرَهُۥ تَقْدِيرًا ﴿٢﴾



(62) Muminai na haƙiƙa (su ne) waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, idan kuma suka kasance tare da shi bisa wani al'amari na jama'a, to ba za su tafi ba har sai sun nemi izininsa. Lalle waɗanda suke neman izininka waɗannan (su ne) waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa. To idan sun nemi izininka saboda wani sha'aninsu, sai ka yi izini ga wanda ka ga dama daga cikinsu, kuma ka nema musu gafarar Allah. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai rahama

(63) Kada ku mayar da kiran Manzo a tsakaninku kamar kiran junanku ga juna[1]. Haƙiƙa Allah Yana sane da waɗanda suke zare jiki daga cikinku a ɓoye. To lalle waɗanda suke saɓa wa umarninsa su ji tsoron kada wata fitina ta shafe su ko kuma wata azaba mai raɗaɗi ta same su

(64) Ku saurara, lalle abin da yake sammai da ƙasa na Allah ne; haƙiƙa Yana sane da abin da ku kuke kansa, da kuma ranar da za a komar da su zuwa gare Shi, sannan Ya ba su labarin abin da suka aikata. Allah Masanin komai ne

Sura Furƙan

(1) (Allah) Wanda Ya saukar wa Bawansa Alƙur'ani don ya zamo mai gargaɗi ga talikai albarkatunsa sun yawaita

(2) (Shi ne) Wanda mulkin sammai da ƙasa nasa ne, kuma bai riƙi wani ɗa ba, ba kuma Shi da wani abokin tarayya a cikin mulkin, Ya kuma halicci kowanne abu, sannan Ya ajiye shi a irin gwargwadon da ya dace da shi

(1) Watau ɗayansu ya riƙa cewa: "Ya Muhammadu" ko "Ya Muhammadu ɗan Abdullahi" ko "Ya ɗan Abdullahi". Sai dai su ce: "Ya Manzon Allah" ko "Ya Annabin Allah".


وَٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةً لَّا يَخْلُقُونَ شَيْـًٔا وَهُمْ يُخْلَقُونَ
وَلَا يَمْلِكُونَ لِأَنفُسِهِمْ ضَرًّا وَلَا نَفْعًا وَلَا يَمْلِكُونَ مَوْتًا
وَلَا حَيَوٰةً وَلَا نُشُورًا ﴿٣﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ إِنْ هَٰذَآ إِلَّآ
إِفْكٌ ٱفْتَرَىٰهُ وَأَعَانَهُۥ عَلَيْهِ قَوْمٌ ءَاخَرُونَ ۖ فَقَدْ جَآءُو ظُلْمًا
وَزُورًا ﴿٤﴾ وَقَالُوٓا۟ أَسَٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ ٱكْتَتَبَهَا فَهِىَ تُمْلَىٰ
عَلَيْهِ بُكْرَةً وَأَصِيلًا ﴿٥﴾ قُلْ أَنزَلَهُ ٱلَّذِى يَعْلَمُ ٱلسِّرَّ
فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٦﴾
وَقَالُوا۟ مَالِ هَٰذَا ٱلرَّسُولِ يَأْكُلُ ٱلطَّعَامَ وَيَمْشِى فِى
ٱلْأَسْوَاقِ ۙ لَوْلَآ أُنزِلَ إِلَيْهِ مَلَكٌ فَيَكُونَ مَعَهُۥ نَذِيرًا ﴿٧﴾
أَوْ يُلْقَىٰٓ إِلَيْهِ كَنزٌ أَوْ تَكُونُ لَهُۥ جَنَّةٌ يَأْكُلُ مِنْهَا ۚ وَقَالَ
ٱلظَّٰلِمُونَ إِن تَتَّبِعُونَ إِلَّا رَجُلًا مَّسْحُورًا ﴿٨﴾ ٱنظُرْ
كَيْفَ ضَرَبُوا۟ لَكَ ٱلْأَمْثَالَ فَضَلُّوا۟ فَلَا يَسْتَطِيعُونَ
سَبِيلًا ﴿٩﴾ تَبَارَكَ ٱلَّذِىٓ إِن شَآءَ جَعَلَ لَكَ خَيْرًا مِّن ذَٰلِكَ
جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ وَيَجْعَل لَّكَ قُصُورًا ﴿١٠﴾ بَلْ
كَذَّبُوا۟ بِٱلسَّاعَةِ ۖ وَأَعْتَدْنَا لِمَن كَذَّبَ بِٱلسَّاعَةِ سَعِيرًا ﴿١١﴾

(3) Kuma suka rifi ababen bauta ba Shi ba, ba sa halittar komai, alhali kuwa su ake halittawa, kuma ba sa mallakar cuta ko amfani ga kawunansu, ba sa kuma mallakar kashewa ko rayawa ko tashi (bayan mutuwa)
(4) Wadanda kuma suka kafirta suka ce: “Wannan (Alkur’ani) ba komai ba ne sai karya da ya kage ta kuma wasu mutane daban suka taimake shi a kansa.” To hakika sun zo da zalunci da kuma karya
(5) Suka kuma ce: “Tatsuniyoyin mutanen farko ne da ya rubuta su, wadanda ake masa shiftar su safe da yamma.”
(6) Ka ce (da su): “Wanda Yake sane da asirin sammai da kasa Shi Ya saukar da shi. Lalle Shi Ya kasance Mai gafara ne, Mai jin kai.”
(7) Suka kuma ce: “Me ya sa wannan Manzo yake cin abinci kuma yake tafiya cikin kasuwanni? Me ya hana a saukar masa da mala’ika, sai ya zama mai gargadi tare da shi?
(8) Ko a jefo masa wata taskar dukiya ko ya zama yana da wani lambu wanda daga gare shi zai rika ci?” Sai azzalumai suka ce “Ba wanda kuke bi sai wani mutum wanda aka yi wa sihiri!”
(9) To ka dubi yadda suka rika buga maka misali[1], sai suka ɓata, don haka ba za su iya bin hanyar shiriya ba
(10) Albarkatun (Allah) sun yawaita, wanda idan Ya ga dama sai Ya sanya maka alheri fiye da wadannan: (su ne) gonakai wadanda koramu suke gudana ta karkashinsu, Ya kuma sanya maka maka-makan gidaje
(11) Ba haka ba ne, sun dai karyata tashin alkiyama ne; Mun kuwa tanadi (wutar) Sa’ira ga wanda ya karyata tashin alkiyama

(1) Watau wani lokaci su ce masa mai sihiri, wani lokaci kuma su ce mawaki, ko su ce boka, ko mai taɓin hankali.

إِذَا رَأَتْهُم مِّن مَّكَانٍۭ بَعِيدٍ سَمِعُوا۟ لَهَا تَغَيُّظًا وَزَفِيرًا ﴿١٢﴾
وَإِذَآ أُلْقُوا۟ مِنْهَا مَكَانًا ضَيِّقًا مُّقَرَّنِينَ دَعَوْا۟ هُنَالِكَ ثُبُورًا
﴿١٣﴾ لَّا تَدْعُوا۟ ٱلْيَوْمَ ثُبُورًا وَٰحِدًا وَٱدْعُوا۟ ثُبُورًا كَثِيرًا ﴿١٤﴾
قُلْ أَذَٰلِكَ خَيْرٌ أَمْ جَنَّةُ ٱلْخُلْدِ ٱلَّتِى وُعِدَ ٱلْمُتَّقُونَ ۚ كَانَتْ
لَهُمْ جَزَآءً وَمَصِيرًا ﴿١٥﴾ لَّهُمْ فِيهَا مَا يَشَآءُونَ خَٰلِدِينَ ۚ
كَانَ عَلَىٰ رَبِّكَ وَعْدًا مَّسْـُٔولًا ﴿١٦﴾ وَيَوْمَ يَحْشُرُهُمْ وَمَا
يَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ فَيَقُولُ ءَأَنتُمْ أَضْلَلْتُمْ عِبَادِى
هَٰٓؤُلَآءِ أَمْ هُمْ ضَلُّوا۟ ٱلسَّبِيلَ ﴿١٧﴾ قَالُوا۟ سُبْحَٰنَكَ مَا كَانَ
يَنۢبَغِى لَنَآ أَن نَّتَّخِذَ مِن دُونِكَ مِنْ أَوْلِيَآءَ وَلَٰكِن مَّتَّعْتَهُمْ
وَءَابَآءَهُمْ حَتَّىٰ نَسُوا۟ ٱلذِّكْرَ وَكَانُوا۟ قَوْمًۢا بُورًا ﴿١٨﴾
فَقَدْ كَذَّبُوكُم بِمَا تَقُولُونَ فَمَا تَسْتَطِيعُونَ صَرْفًا
وَلَا نَصْرًا ۚ وَمَن يَظْلِم مِّنكُمْ نُذِقْهُ عَذَابًا كَبِيرًا ﴿١٩﴾
وَمَآ أَرْسَلْنَا قَبْلَكَ مِنَ ٱلْمُرْسَلِينَ إِلَّآ إِنَّهُمْ لَيَأْكُلُونَ
ٱلطَّعَامَ وَيَمْشُونَ فِى ٱلْأَسْوَاقِ ۗ وَجَعَلْنَا بَعْضَكُمْ
لِبَعْضٍ فِتْنَةً أَتَصْبِرُونَ ۗ وَكَانَ رَبُّكَ بَصِيرًا ﴿٢٠﴾

(12) Idan (wutar) ta hango su daga wuri mai nisa sai su ji tafarfasa da gurnaninta
(13) Idan kuwa aka jefa su cikinta a wani wuri kuntatacce nata, suna kukunce, sai su rika kiran hallaka a can
(14) (Sai a ce da su): "A yau kada ku kirawo hallaka daya kawai, ku kirawo hallaka da yawa!"
(15) Ka ce (da su): "Yanzu wannan ne ya fi alheri, ko kuwa Aljannar dawwama wadda aka yi wa masu takawa alkawarinta, ta zama sakamako da makoma a gare su?"
(16) Suna da duk abin da suka ga dama a cikinta, masu dawwama ne. (Wannan kuma) ya kasance alkawari ne abin tambaya a kan Ubangijnka
(17) (Ka tuna) kuma ranar da zai tara su da abin da suke bauta wa ba Allah ba, sai Ya ce (da su): "Shin yanzu ku ne kuka batar da bayina wadannan, ko kuwa su ne suka bace wa hanya don kansu?"(18) Suka ce: "Tsarki ya tabbata gare Ka, bai zamanto ya dace da mu ba mu riki wasu majibinta ba Kai ba, sai dai kuma Ka jiyar da su dadi ne tare da iyayensu har suka manta tuna Ka, suka kuwa kasance mutane hallakakku."
(19) To hakika sun karyata ku game da abin da kuke fada, to ba za ku samu wata makauta ba, ko kuma wani taimako. Duk wanda kuma ya yi zalunci daga cikinku za Mu dandana masa azaba mai girma
(20) Kuma ba Mu aiko manzanni ba gabaninka sai cewa lalle suna cin abinci kuma suna tafiya cikin kasuwanni. Mun kuwa sanya wasunku su zama fitina ga wasu. Shin za ku yi hakuri? Ubangijinka kuwa Ya kasance Mai gani ne


* وَقَالَ ٱلَّذِينَ لَا يَرۡجُونَ لِقَآءَنَا لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡنَا ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ
أَوۡ نَرَىٰ رَبَّنَاۗ لَقَدِ ٱسۡتَكۡبَرُواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۡ وَعَتَوۡ عُتُوّٗا كَبِيرٗا
٢١ يَوۡمَ يَرَوۡنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ لَا بُشۡرَىٰ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُجۡرِمِينَ وَيَقُولُونَ
حِجۡرٗا مَّحۡجُورٗا ٢٢ وَقَدِمۡنَآ إِلَىٰ مَا عَمِلُواْ مِنۡ عَمَلٖ فَجَعَلۡنَٰهُ
هَبَآءٗ مَّنثُورًا ٢٣ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِ يَوۡمَئِذٍ خَيۡرٞ مُّسۡتَقَرّٗا
وَأَحۡسَنُ مَقِيلٗا ٢٤ وَيَوۡمَ تَشَقَّقُ ٱلسَّمَآءُ بِٱلۡغَمَٰمِ وَنُزِّلَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ
تَنزِيلًا ٢٥ ٱلۡمُلۡكُ يَوۡمَئِذٍ ٱلۡحَقُّ لِلرَّحۡمَٰنِۚ وَكَانَ يَوۡمًا عَلَى
ٱلۡكَٰفِرِينَ عَسِيرٗا ٢٦ وَيَوۡمَ يَعَضُّ ٱلظَّالِمُ عَلَىٰ يَدَيۡهِ يَقُولُ
يَٰلَيۡتَنِي ٱتَّخَذۡتُ مَعَ ٱلرَّسُولِ سَبِيلٗا ٢٧ يَٰوَيۡلَتَىٰ لَيۡتَنِي لَمۡ
أَتَّخِذۡ فُلَانًا خَلِيلٗا ٢٨ لَّقَدۡ أَضَلَّنِي عَنِ ٱلذِّكۡرِ بَعۡدَ إِذۡ جَآءَنِيۗ
وَكَانَ ٱلشَّيۡطَٰنُ لِلۡإِنسَٰنِ خَذُولٗا ٢٩ وَقَالَ ٱلرَّسُولُ يَٰرَبِّ
إِنَّ قَوۡمِي ٱتَّخَذُواْ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانَ مَهۡجُورٗا ٣٠ وَكَذَٰلِكَ
جَعَلۡنَا لِكُلِّ نَبِيٍّ عَدُوّٗا مِّنَ ٱلۡمُجۡرِمِينَۗ وَكَفَىٰ بِرَبِّكَ هَادِيٗا
وَنَصِيرٗا ٣١ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَوۡلَا نُزِّلَ عَلَيۡهِ ٱلۡقُرۡءَانُ جُمۡلَةٗ
وَٰحِدَةٗۚ كَذَٰلِكَ لِنُثَبِّتَ بِهِۦ فُؤَادَكَۖ وَرَتَّلۡنَٰهُ تَرۡتِيلٗا ٣٢

(21) Wadanda kuma ba sa tsammanin haduwa da Mu suka ce: “Me ya hana a saukar mana da mala’iku ko kuma mu ga Ubangijinmu?” Hakika lalle sun yi girman kai don (suna) ji da kawunansu, suka kuma yi tsaurin kai babba kwarai da gaske

(22) Ranar da za su ga mala’iku[1] a wannan ranar babu wani farin ciki ga masu laifi, za kuma su rika cewa: “(Albishir daga Allah) haramun ne abin haramtawa ne (a gare su)”

(23) Muka kuma gabato zuwa ga d[illegible]nai da shi kura abar daidaitawa

(24) ‘Yan Aljanna a wannan ranar su suka fi kyakkyawan mazauni kuma suka fi kyawon wurin barcin kailula[2]

(25) Kuma (ka tuna) ranar da sama za ta kekkece da girgije, kuma a saukar da mala’iku gungu-gungu

(26) Mulki tabbatacce a wannan ranar na (Allah) Mai rahama ne. Kuma ta kasance rana ce mawuyaciya ga kafurai

(27) (Ka tuna) kuma ranar da azzalumi zai rika cizon yatsunsa yana cewa: “Ina ma na bi hanya tare da Manzo!

(28) “Kaicona ina ma da ban riki wane aboki ba!

(29) “Hakika ya batar da ni daga bin Alkur’ani, bayan ya zo mini.” Shaidan kuwa ya kasance mai tabar da mutum ne

(30) Manzo kuma ya ce: “Ya Ubangijina, lalle mutanena sun riki wannan Alkur’ani abin kaurace wa[3].”

(31) Kamar haka Muka sanya wa kowanne annabi abokan gaba daga masu laifi, kuma Ubangijinka Ya ishe ka Mai shiryarwa Mai taimako

(32) Wadanda kuma suka kafirta suka ce: “Me ya hana a saukar masa da Alkur’ani gaba daya, a lokaci guda[4]?” Kamar haka ne (Muke saukar da shi kadan-kadan) don Mu tabbatar da zuciyarka da shi, Muka kuma karantar (da kai) shi daki-daki

(1) Watau ranar mutuwarsu ko a cikin kaburburansu da ranar da za a kora su domin yi musu hisabi.

(2) Domin za a gama hisabi gabanin lokacin azahar, har ‘yan Aljanna za su shige ta su riski lokacin kailula a cikinta.

(3) Watau ta hanyar guje wa sauraron sa da rashin karanta shi da aiki da koyarwarsa.

(4) Watau kamar yadda aka saukar da littafin Attaura ko Linjila.

وَلَا يَأْتُونَكَ بِمَثَلٍ إِلَّا جِئْنَاكَ بِالْحَقِّ وَأَحْسَنَ تَفْسِيرًا ﴿٣٣﴾ الَّذِينَ يُحْشَرُونَ عَلَىٰ وُجُوهِهِمْ إِلَىٰ جَهَنَّمَ أُولَٰئِكَ شَرٌّ مَّكَانًا وَأَضَلُّ سَبِيلًا ﴿٣٤﴾ وَلَقَدْ آتَيْنَا مُوسَى الْكِتَابَ وَجَعَلْنَا مَعَهُ أَخَاهُ هَارُونَ وَزِيرًا ﴿٣٥﴾ فَقُلْنَا اذْهَبَا إِلَى الْقَوْمِ الَّذِينَ كَذَّبُوا بِآيَاتِنَا فَدَمَّرْنَاهُمْ تَدْمِيرًا ﴿٣٦﴾ وَقَوْمَ نُوحٍ لَّمَّا كَذَّبُوا الرُّسُلَ أَغْرَقْنَاهُمْ وَجَعَلْنَاهُمْ لِلنَّاسِ آيَةً ۖ وَأَعْتَدْنَا لِلظَّالِمِينَ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿٣٧﴾ وَعَادًا وَثَمُودَ وَأَصْحَابَ الرَّسِّ وَقُرُونًا بَيْنَ ذَٰلِكَ كَثِيرًا ﴿٣٨﴾ وَكُلًّا ضَرَبْنَا لَهُ الْأَمْثَالَ ۖ وَكُلًّا تَبَّرْنَا تَتْبِيرًا ﴿٣٩﴾ وَلَقَدْ أَتَوْا عَلَى الْقَرْيَةِ الَّتِي أُمْطِرَتْ مَطَرَ السَّوْءِ ۚ أَفَلَمْ يَكُونُوا يَرَوْنَهَا بَلْ كَانُوا لَا يَرْجُونَ نُشُورًا ﴿٤٠﴾ وَإِذَا رَأَوْكَ إِن يَتَّخِذُونَكَ إِلَّا هُزُوًا أَهَٰذَا الَّذِي بَعَثَ اللَّهُ رَسُولًا ﴿٤١﴾ إِن كَادَ لَيُضِلُّنَا عَنْ آلِهَتِنَا لَوْلَا أَن صَبَرْنَا عَلَيْهَا ۚ وَسَوْفَ يَعْلَمُونَ حِينَ يَرَوْنَ الْعَذَابَ مَنْ أَضَلُّ سَبِيلًا ﴿٤٢﴾ أَرَأَيْتَ مَنِ اتَّخَذَ إِلَٰهَهُ هَوَاهُ أَفَأَنتَ تَكُونُ عَلَيْهِ وَكِيلًا ﴿٤٣﴾

(33) Kuma ba za su zo maka da wani misali ba (na ƙalu-bale) sai Mun zo maka da gaskiya, kuma da mafi kyan bayani

(34) Waɗanda za a tashe su zuwa wutar Jahannama a kan fuskokinsu, waɗannan su suka fi mummunan matsayi kuma mafiya ɓatacciyar hanya

(35) Haƙiƙa kuma Mun bai wa Musa Littafi muka kuma sanya ɗan'uwansa Haruna tare da shi a matsayin Waziri

(36) Sai Muka ce: "Ku tafi zuwa ga mutanen da suka ƙaryata ayoyinmu, sai Muka hallaka su hallakarwa mai tsanani!"

(37) Mutanen Nuhu kuma lokacin da suka ƙaryata manzanni[1] sai Muka nutsar da su, Muka kuma sanya su wa'azi ga mutane, kuma Muka tanadi azaba mai raɗaɗi ga azzalumai

(38) Kuma (Muka hallakar da) Adawa da Samudawa da kuma mutanen (rijiyar) Rassu, da kuma wasu al'ummu masu yawa tsakanin hakan

(39)Kowannensu kuwa Mun ba shi misalai; kuma kowannensu Mun hallaka shi mummunar hallakawa

(40) Haƙiƙa kuma (su mutanen Makka) sun bi ta alƙaryar nan wadda aka yi wa ruwan azaba. Shin ba su kasance suna ganin ta ba ne? Ba haka ba ne, sun dai kasance ne ba sa tsammanin tashin alƙiyama

(41) Idan kuma suka gan ka ba sa rikon ka sai abin yi wa izgili, (suna cewa): "Yanzu wannan ne wanda Allah ya aiko Manzo?

(42) "Lalle saura ƙiris ya ɓatar da mu daga ababen bautarmu, ba don mun yi haƙuri a kansu ba." Ba da daɗewa ba kuwa za su san wanda ya fi ɓatan hanya yayin da za su ga azaba (43) Shin ka ga wanda ya mayar da son zuciyarsa (shi ne) abin bautarsa, to yanzu kai za ka zama mai kiyaye shi (daga bin son zuciyarsa)?

(1) Watau ta hanyar ƙaryata Annabi Nuhu( ), domin saƙon duk manzanni guda ɗaya ne, shi ne kaɗaita Allah da bauta.

أَمْ تَحْسَبُ أَنَّ أَكْثَرَهُمْ يَسْمَعُونَ أَوْ يَعْقِلُونَ ۚ إِنْ هُمْ إِلَّا
كَٱلْأَنْعَٰمِ بَلْ هُمْ أَضَلُّ سَبِيلًا ﴿٤٤﴾ أَلَمْ تَرَ إِلَىٰ رَبِّكَ كَيْفَ مَدَّ
ٱلظِّلَّ وَلَوْ شَآءَ لَجَعَلَهُۥ سَاكِنًا ثُمَّ جَعَلْنَا ٱلشَّمْسَ عَلَيْهِ دَلِيلًا
﴿٤٥﴾ ثُمَّ قَبَضْنَٰهُ إِلَيْنَا قَبْضًا يَسِيرًا ﴿٤٦﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ
ٱلَّيْلَ لِبَاسًا وَٱلنَّوْمَ سُبَاتًا وَجَعَلَ ٱلنَّهَارَ نُشُورًا ﴿٤٧﴾ وَهُوَ
ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ ٱلرِّيَٰحَ بُشْرًۢا بَيْنَ يَدَىْ رَحْمَتِهِۦ ۚ وَأَنزَلْنَا مِنَ
ٱلسَّمَآءِ مَآءً طَهُورًا ﴿٤٨﴾ لِّنُحْيِىَ بِهِۦ بَلْدَةً مَّيْتًا وَنُسْقِيَهُۥ
مِمَّا خَلَقْنَآ أَنْعَٰمًا وَأَنَاسِىَّ كَثِيرًا ﴿٤٩﴾ وَلَقَدْ صَرَّفْنَٰهُ بَيْنَهُمْ
لِيَذَّكَّرُوا۟ فَأَبَىٰٓ أَكْثَرُ ٱلنَّاسِ إِلَّا كُفُورًا ﴿٥٠﴾ وَلَوْ شِئْنَا
لَبَعَثْنَا فِى كُلِّ قَرْيَةٍ نَّذِيرًا ﴿٥١﴾ فَلَا تُطِعِ ٱلْكَٰفِرِينَ وَجَٰهِدْهُم
بِهِۦ جِهَادًا كَبِيرًا ﴿٥٢﴾ ۞ وَهُوَ ٱلَّذِى مَرَجَ ٱلْبَحْرَيْنِ هَٰذَا
عَذْبٌ فُرَاتٌ وَهَٰذَا مِلْحٌ أُجَاجٌ وَجَعَلَ بَيْنَهُمَا بَرْزَخًا
وَحِجْرًا مَّحْجُورًا ﴿٥٣﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى خَلَقَ مِنَ ٱلْمَآءِ بَشَرًا فَجَعَلَهُۥ
نَسَبًا وَصِهْرًا ۗ وَكَانَ رَبُّكَ قَدِيرًا ﴿٥٤﴾ وَيَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
مَا لَا يَنفَعُهُمْ وَلَا يَضُرُّهُمْ ۗ وَكَانَ ٱلْكَافِرُ عَلَىٰ رَبِّهِۦ ظَهِيرًا ﴿٥٥﴾

(44)Ko kuwa kana tsammanin cewa yawancinsu suna ji ne (na fahimta) ko suna hankalta? Ai su ba wasu ba ne illa kamar dabbobi; a'a su ne ma suka fi (dabbobi) ɓace hanya. (45)Shin ba ka ganin (irin aikin) Ubangijinka yadda ya shimfiɗa inuwa, da kuwa ya ga dama da sai ya sanya ta a tsaye cak, sannan Muka sanya rana dalilin samuwarta (inuwar)
(46) Sannan Muka riƙa janye ta da kaɗan-kaɗan[1]
(47) Kuma shi ne wanda ya sanya muku dare ya zama sutura, bacci kuma don hutawa kuma ya sanya rana don watsuwa (wajen neman abinci)

(48) Kuma shi ne wanda ya aiko iska don albishir a gabanin (saukar) rahamarsa. Muka kuma saukar da ruwa mai tsarkakewa daga sama (49) Don Mu raya busasshiyar ƙasa da shi, kuma Mu shayar da dabbobi da mutane masu yawa daga abubuwan da Muka halitta (50) Haƙiƙa kuma Mun sarrafa shi a tsakaninsu don su wa'azantu[2], sai mafi yawan mutane suka ƙi (wa'azantuwa) sai kafirci(51) Da kuma Mun ga dama, lalle da mun aiko wani mai gargaɗi cikin kowacce alƙarya[3](52) To kada ka bi son ran kafirai kuma ka yaƙe su da shi (Alƙur'ani) yaƙi mai girma(53) Shi ne kuma wanda Ya haɗa koguna biyu: wannan mai tsananin daɗi wannan kuma mai tsananin zartsi, Ya kuma sanya shamaki a tsakaninsu da kuma kariya mai karewa(54) Shi ne kuma wanda Ya halicci mutum daga ruwa sannan Ya mayar da shi dangantaka da surukuta. Ubangijinka Ya kasance Mai iko ne (55) Kuma suna bauta wa wanin Allah abin da ba zai amfane su ba kuma ba zai cuce su ba. Kafiri kuwa ya kasance mai taimaka wa (Shaiɗan ne) a kan bijire wa Ubangijinsa

(1) Watau tana raguwa gwargwadon ɗagawar rana, har ya zamanto ta gushe gaba ɗaya.

(2) Watau Allah ( ) ya sarrafa hujjoji da dalilai daban-daban a cikin Alƙur'ani domin mutane su wa'azantu.

(3) Amma bai yi haka ba, sai ya aiko Annabi Muhammadu ( ) shi kaɗai zuwa ga talikai baki ɗaya.

وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا مُبَشِّرٗا وَنَذِيرٗا ٥٦ قُلۡ مَآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ
مِنۡ أَجۡرٍ إِلَّا مَن شَآءَ أَن يَتَّخِذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ سَبِيلٗا ٥٧ وَتَوَكَّلۡ
عَلَى ٱلۡحَيِّ ٱلَّذِي لَا يَمُوتُ وَسَبِّحۡ بِحَمۡدِهِۦۚ وَكَفَىٰ بِهِۦ
بِذُنُوبِ عِبَادِهِۦ خَبِيرًا ٥٨ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ
وَمَا بَيۡنَهُمَا فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰ عَلَى ٱلۡعَرۡشِۖ ٱلرَّحۡمَٰنُ
فَسۡـَٔلۡ بِهِۦ خَبِيرٗا ٥٩ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱسۡجُدُواْ لِلرَّحۡمَٰنِ قَالُواْ
وَمَا ٱلرَّحۡمَٰنُ أَنَسۡجُدُ لِمَا تَأۡمُرُنَا وَزَادَهُمۡ نُفُورَۢا ٦٠ تَبَارَكَ
ٱلَّذِي جَعَلَ فِي ٱلسَّمَآءِ بُرُوجٗا وَجَعَلَ فِيهَا سِرَٰجٗا وَقَمَرٗا
مُّنِيرٗا ٦١ وَهُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ خِلۡفَةٗ لِّمَنۡ أَرَادَ
أَن يَذَّكَّرَ أَوۡ أَرَادَ شُكُورٗا ٦٢ وَعِبَادُ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلَّذِينَ يَمۡشُونَ
عَلَى ٱلۡأَرۡضِ هَوۡنٗا وَإِذَا خَاطَبَهُمُ ٱلۡجَٰهِلُونَ قَالُواْ سَلَٰمٗا
٦٣ وَٱلَّذِينَ يَبِيتُونَ لِرَبِّهِمۡ سُجَّدٗا وَقِيَٰمٗا ٦٤ وَٱلَّذِينَ
يَقُولُونَ رَبَّنَا ٱصۡرِفۡ عَنَّا عَذَابَ جَهَنَّمَۖ إِنَّ عَذَابَهَا كَانَ
غَرَامًا ٦٥ إِنَّهَا سَآءَتۡ مُسۡتَقَرّٗا وَمُقَامٗا ٦٦ وَٱلَّذِينَ إِذَآ
أَنفَقُواْ لَمۡ يُسۡرِفُواْ وَلَمۡ يَقۡتُرُواْ وَكَانَ بَيۡنَ ذَٰلِكَ قَوَامٗا ٦٧

(56) Kuma ba Mu aiko ka ba sai kawai don ka zama mai albishir mai gargaɗi
(57) Ka ce (da su): “Ba na tambayar ku wani lada a kansa (gargaɗin), sai dai ya rage ga wanda ya ga dama ya riƙi hanya (ta gari) zuwa ga Ubangijinsa.”
(58) Kuma ka dogara ga (Allah) Rayayye Wanda ba zai mutu ba, kuma ka yi tasbihi da godiyar sa, kuma Ya isa Masani ga zunuban bayinsa
(59) (Shi ne) wanda Ya halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu cikin kwana shida, sannan Ya daidaita a kan Al’arshi. (Shi ne) Arrahmanu, sai ka tambayi Masani game da Shi
(60) Idan kuwa aka ce da su: “Ku yi sujjada ga Arrahmanu” sai su ce: “Mene ne Arrahmanu(1)? Yanzu ma yi sujjada ga abin da kake umartar mu?” (Wannan umarnin) kuma ya ƙara musu fanɗarewa
(61) Wanda Ya sanya wuraren saukar taurari cikin sama, Ya kuma sanya mata rana mai haske da wata mai haskakawa(2), albarkatunsa sun yawaita
(62) Shi ne kuma wanda Ya sanya dare da rana masu maye wa juna ga wanda ya yi nufin ya wa’azantu ko kuma ya yi nufin godiya
(63) Bayin (Allah) Mai rahama kuwa (su ne) waɗanda suke tafiya a bayan ƙasa a natse; idan kuma wawaye sun yi musu magana (sai) su faɗa (musu) magana ta aminci
(64) (Su ne) kuma waɗanda suke kwana suna masu sujjada da tsayuwa ga Ubangijinsu
(65) (Su ne) kuma waɗanda suke cewa: “Ya Ubangijinmu, Ka kawar mana da azabar Jahannama; lalle azabarta ta kasance halaka ce mai ɗorewa
(66) “Lalle ita (Jahannama) ta kasance mummunar matabbata kuma mazauna (ga kafirai).”
(67) (Su ne) kuma waɗanda idan suka ciyar ba sa almubazzaranci kuma ba sa yin ƙwauro, (ciyarwarsu) kuwa ta kasance tsaka-tsaki ce

(1) Watau kafirai ba su yarda da sunan Allah Arrahmanu ba, kamar yadda ya zo a cikin Suratur Ra’ad, aya ta 30.

(2) Watau rana mai xauke da haske a karan-kanta da kuma wata wanda yake samun haskensa daga hasken rana.

وَٱلَّذِينَ لَا يَدۡعُونَ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ وَلَا يَقۡتُلُونَ ٱلنَّفۡسَ
ٱلَّتِي حَرَّمَ ٱللَّهُ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَلَا يَزۡنُونَۚ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ
يَلۡقَ أَثَامٗا ٦٨ يُضَٰعَفۡ لَهُ ٱلۡعَذَابُ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَيَخۡلُدۡ
فِيهِۦ مُهَانًا ٦٩ إِلَّا مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ عَمَلٗا صَٰلِحٗا
فَأُوْلَٰٓئِكَ يُبَدِّلُ ٱللَّهُ سَيِّـَٔاتِهِمۡ حَسَنَٰتٖۗ وَكَانَ ٱللَّهُ
غَفُورٗا رَّحِيمٗا ٧٠ وَمَن تَابَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا فَإِنَّهُۥ يَتُوبُ
إِلَى ٱللَّهِ مَتَابٗا ٧١ وَٱلَّذِينَ لَا يَشۡهَدُونَ ٱلزُّورَ وَإِذَا مَرُّواْ
بِٱللَّغۡوِ مَرُّواْ كِرَامٗا ٧٢ وَٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِّرُواْ بِـَٔايَٰتِ
رَبِّهِمۡ لَمۡ يَخِرُّواْ عَلَيۡهَا صُمّٗا وَعُمۡيَانٗا ٧٣ وَٱلَّذِينَ يَقُولُونَ
رَبَّنَا هَبۡ لَنَا مِنۡ أَزۡوَٰجِنَا وَذُرِّيَّٰتِنَا قُرَّةَ أَعۡيُنٖ وَٱجۡعَلۡنَا
لِلۡمُتَّقِينَ إِمَامًا ٧٤ أُوْلَٰٓئِكَ يُجۡزَوۡنَ ٱلۡغُرۡفَةَ بِمَا صَبَرُواْ
وَيُلَقَّوۡنَ فِيهَا تَحِيَّةٗ وَسَلَٰمًا ٧٥ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ
حَسُنَتۡ مُسۡتَقَرّٗا وَمُقَامٗا ٧٦ قُلۡ مَا يَعۡبَؤُاْ بِكُمۡ رَبِّي
لَوۡلَا دُعَآؤُكُمۡۖ فَقَدۡ كَذَّبۡتُمۡ فَسَوۡفَ يَكُونُ لِزَامٗا ٧٧
سُورَةُ الشُّعَرَاءِ

(68) (Su ne) kuma waɗanda ba sa bauta wa wani tare da Allah, kuma ba sa kashe ran da Allah Ya hana kashewa sai da haƙƙi, kuma ba sa yin zina. Wanda kuwa ya aikata hakan to zai haɗu da (uƙubar) laifinsa

(69) Za a ninninka masa azaba ranar alƙiyama, kuma ya dawwama a cikinta a wulaƙance

(70) Sai dai wanda ya tuba ya kuma yi imani, kuma ya yi aiki na gari, to waɗannan Allah zai musanya munanan ayyukansu da kyawawa. Allah kuwa ya kasance Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(71) Wanda kuwa ya tuba ya kuma yi aiki na gari, to lalle shi ne wanda yake tuba na gaskiya zuwa ga Allah

(72) (Su ne) kuma waɗanda ba sa halartar wuraren baɗala, idan kuma suka wuce ta wurin aikin assha to sai su wuce suna masu mutunta kansu)

(73) (Su ne) kuma waɗanda idan aka yi musu wa'azi da ayoyin Ubangijinsu ba sa fuskantar su suna kurame kuma makafi

(74) (Su ne) kuma waɗanda suke cewa: "Ya Ubangijinmu, Ka ba mu masu sanyaya mana zukata daga matayenmu da zuri'armu, kuma Ka sanya mu abin koyi ga masu taƙawa

(75) Waɗannan su ne ake saka wa da ɗakuna na Aljanna saboda haƙurin da suka yi, za kuma a tare su a cikinta da gaisuwa da sallama

(76) Suna madawwama a cikinta. Matabbata da mazauni sun kyautata

(77) Ka ce: "Ba ruwan Ubangijina da ku in ba don ibadarku ba; to ga shi kun ƙaryata, to wannan (sakamakonsa) zai zama azaba ce mai ɗorewa[1]."

(1) Watau ba domin bayinsa na gari waxanda suke bauta masa kuma suna roqon sa ba, da ba ruwansa da su domin sun qaryataManzon Allah ( ).

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

طسٓمٓ ﴿١﴾ تِلْكَ ءَايَٰتُ ٱلْكِتَٰبِ ٱلْمُبِينِ ﴿٢﴾ لَعَلَّكَ بَٰخِعٌ نَّفْسَكَ أَلَّا
يَكُونُوا۟ مُؤْمِنِينَ ﴿٣﴾ إِن نَّشَأْ نُنَزِّلْ عَلَيْهِم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ ءَايَةً فَظَلَّتْ
أَعْنَٰقُهُمْ لَهَا خَٰضِعِينَ ﴿٤﴾ وَمَا يَأْتِيهِم مِّن ذِكْرٍ مِّنَ ٱلرَّحْمَٰنِ مُحْدَثٍ
إِلَّا كَانُوا۟ عَنْهُ مُعْرِضِينَ ﴿٥﴾ فَقَدْ كَذَّبُوا۟ فَسَيَأْتِيهِمْ أَنۢبَٰٓؤُا۟ مَا كَانُوا۟
بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿٦﴾ أَوَلَمْ يَرَوْا۟ إِلَى ٱلْأَرْضِ كَمْ أَنۢبَتْنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوْجٍ
كَرِيمٍ ﴿٧﴾ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً ۖ وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٨﴾ وَإِنَّ
رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٩﴾ وَإِذْ نَادَىٰ رَبُّكَ مُوسَىٰٓ أَنِ ٱئْتِ ٱلْقَوْمَ
ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٠﴾ قَوْمَ فِرْعَوْنَ ۚ أَلَا يَتَّقُونَ ﴿١١﴾ قَالَ رَبِّ إِنِّىٓ أَخَافُ
أَن يُكَذِّبُونِ ﴿١٢﴾ وَيَضِيقُ صَدْرِى وَلَا يَنطَلِقُ لِسَانِى فَأَرْسِلْ
إِلَىٰ هَٰرُونَ ﴿١٣﴾ وَلَهُمْ عَلَىَّ ذَنۢبٌ فَأَخَافُ أَن يَقْتُلُونِ ﴿١٤﴾ قَالَ
كَلَّا ۖ فَٱذْهَبَا بِـَٔايَٰتِنَآ ۖ إِنَّا مَعَكُم مُّسْتَمِعُونَ ﴿١٥﴾ فَأْتِيَا فِرْعَوْنَ
فَقُولَآ إِنَّا رَسُولُ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٦﴾ أَنْ أَرْسِلْ مَعَنَا بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ
﴿١٧﴾ قَالَ أَلَمْ نُرَبِّكَ فِينَا وَلِيدًا وَلَبِثْتَ فِينَا مِنْ عُمُرِكَ سِنِينَ
﴿١٨﴾ وَفَعَلْتَ فَعْلَتَكَ ٱلَّتِى فَعَلْتَ وَأَنتَ مِنَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿١٩﴾

Sura Shu'ara

(1) ƊA SIN MIM
(2) Waƌannan ayoyi ne na Littafi mabayyani
(3) Ko za ka kashe kanka ne don ba su zama muminai ba?
(4) Da Mun ga dama da sai Mu saukar musu da aya daga sama sai wuyoyinsu su zamo masu ƙanƙan da kai gare ta[1]
(5) Kuma ba wani wa'azi sabo da zai zo musu daga (Allah) Mai rahama sai sun kasance masu bijire masa
(6) To haƙiƙa sun ƙaryata, ba da daƌewa ba labaran aƙibar abin da suke yi wa izgili za su zo musu
(7) Shin ba su yi duba zuwa ga ƙasa ba, (su ga) dangogin tsirrai masu kyau nawa ne Muka tsirar daga cikinta?
(8) Lalle a game da wannan tabbas akwai aya (mai nuna cikar ikon Allah); kuma yawancinsu ba su zamanto masu imani ba
(9) Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi Mabuwayi ne, Mai rahama
(10) Kuma (ka tuna) lokacin da Ubangijinka Ya kira Musa cewa: "Ka tafi wajen mutanen nan azzalumai
(11) "(Watau) mutanen Fir'auna. Yanzu ba za su kiyaye dokokin Allah ba?"
(12) (Musa) ya ce: "Ya Ubangijina, lalle ni ina tsoron su ƙaryata ni
(13) "Kuma ƙirjina yana ƙuntata, kuma harshena ba ya sakuwa, sai Ka aika zuwa ga (ƌan'uwana) Haruna
(14) "Ni kuma akwai wani laifi da na yi musu, sai nake tsoron su kashe ni."
(15) (Allah) Ya ce: "A'a; (ba abin da zai same ka), sai ku tafi (kai da ƌan'uwanka) da ayoyinmu; lalle Mu masu jin (komai da zai faru) ne tare da ku
(16) "Ku je wajen Fir'auna sai ku faƌa masa cewa: 'Lalle mu manzannin Ubangijin talikai ne
(17) "'Cewa, ka sako mana da Banu-Isra'ila'."
(18) (Fir'auna) ya ce: "Yanzu ba mu muka raine ka a cikinmu tun kana jariri ba, kuma ka zauna ka yi wasu shekaru na rayuwarka a cikinmu?
(19) "Ka kuma aikata aika-aikarka da ka aikata[2] alhali kuwa kana daga masu butulce wa (ni'imata)?"

(1) Watau mu'ujizar da za ta tilasta musu su miqa wuya ko ba sa so.

(2) Yana nufin kashe Baqibxe da ya yi lokacin da ya same shi yana faxa da Ba'isra'ile. Duba Suratul Qasas, ayat ta 15.

قَالَ فَعَلْتُهَآ إِذًا وَأَنَا۠ مِنَ ٱلضَّآلِّينَ ﴿٢٠﴾ فَفَرَرْتُ مِنكُمْ لَمَّا خِفْتُكُمْ
فَوَهَبَ لِى رَبِّى حُكْمًا وَجَعَلَنِى مِنَ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿٢١﴾ وَتِلْكَ نِعْمَةٌ
تَمُنُّهَا عَلَىَّ أَنْ عَبَّدتَّ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿٢٢﴾ قَالَ فِرْعَوْنُ وَمَا رَبُّ ٱلْعَٰلَمِينَ
﴿٢٣﴾ قَالَ رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَآ ۖ إِن كُنتُم مُّوقِنِينَ
﴿٢٤﴾ قَالَ لِمَنْ حَوْلَهُۥٓ أَلَا تَسْتَمِعُونَ ﴿٢٥﴾ قَالَ رَبُّكُمْ وَرَبُّ ءَابَآئِكُمُ
ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٢٦﴾ قَالَ إِنَّ رَسُولَكُمُ ٱلَّذِىٓ أُرْسِلَ إِلَيْكُمْ لَمَجْنُونٌ
﴿٢٧﴾ قَالَ رَبُّ ٱلْمَشْرِقِ وَٱلْمَغْرِبِ وَمَا بَيْنَهُمَآ ۖ إِن كُنتُمْ تَعْقِلُونَ
﴿٢٨﴾ قَالَ لَئِنِ ٱتَّخَذْتَ إِلَٰهًا غَيْرِى لَأَجْعَلَنَّكَ مِنَ ٱلْمَسْجُونِينَ
﴿٢٩﴾ قَالَ أَوَلَوْ جِئْتُكَ بِشَىْءٍ مُّبِينٍ ﴿٣٠﴾ قَالَ فَأْتِ بِهِۦٓ إِن كُنتَ
مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿٣١﴾ فَأَلْقَىٰ عَصَاهُ فَإِذَا هِىَ ثُعْبَانٌ مُّبِينٌ ﴿٣٢﴾
وَنَزَعَ يَدَهُۥ فَإِذَا هِىَ بَيْضَآءُ لِلنَّٰظِرِينَ ﴿٣٣﴾ قَالَ لِلْمَلَإِ حَوْلَهُۥٓ
إِنَّ هَٰذَا لَسَٰحِرٌ عَلِيمٌ ﴿٣٤﴾ يُرِيدُ أَن يُخْرِجَكُم مِّنْ أَرْضِكُم
بِسِحْرِهِۦ فَمَاذَا تَأْمُرُونَ ﴿٣٥﴾ قَالُوٓا۟ أَرْجِهْ وَأَخَاهُ وَٱبْعَثْ فِى ٱلْمَدَآئِنِ
حَٰشِرِينَ ﴿٣٦﴾ يَأْتُوكَ بِكُلِّ سَحَّارٍ عَلِيمٍ ﴿٣٧﴾ فَجُمِعَ ٱلسَّحَرَةُ
لِمِيقَٰتِ يَوْمٍ مَّعْلُومٍ ﴿٣٨﴾ وَقِيلَ لِلنَّاسِ هَلْ أَنتُم مُّجْتَمِعُونَ ﴿٣٩﴾

(20) (Musa) ya ce: "Na aikata haka ne a lokacin ina cikin marasa shiriya (ta rashin wahayi)
(21) "Sannan na guje muku lokacin da na tsorata da ku, sai Ubangijina Ya ba ni kyautar ilimi Ya kuma sanya ni daga manzanni
(22) "Waccen ni'imar kuwa da kake goranta min ita saboda ka bautar da Bani-Isra'ila ne."
(23) Fir'auna ya ce: "To wane ne Ubangijin talikai?"
(24) (Musa) ya ce: "(Shi ne) Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, idan har kun kasance masu sakankancewa (da hakan)"
(25) (Fir'auna) ya ce da waɗanda suke kewaye da shi: "Shin ba kwa jin (abin da yake faɗa)?"
(26) (Musa) ya ce: "Shi ne Ubangijinku kuma Ubangijin iyayenku na farko!"(27) (Fir'auna) ya ce: "Lalle Manzon da aka aiko muku tabbas mai taɓin hankali ne!"
(28) (Musa) ya ce: "(Shi ne) Ubangijin mahudar rana da mafaɗarta da kuma abin da yake tsakaninsu; in kun zamanto masu hankalta."
(29) (Fir'auna) ya ce: "Na rantse in har ka riƙi wani abin bauta ba ni ba, tabbas zan jefa ka cikin 'yan kurkuku!"
(30) (Musa) ya ce: "Ko da na zo maka da wani abu bayyananne?"
(31) (Fir'auna) ya ce: "To ka zo da shi ɗin in ka kasance daga masu gaskiya."
(32) Sannan (Musa) ya jefa sandarsa sai ga ta (ta zama) kumurci ƙuru-ƙuru
(33) Ya kuma zaro hannunsa (daga cikin rigarsa) sai ga shi fari fat ga masu gani (34) (Sai Fir'auna) ya ce da manyan mutanen da ke kewaye da shi: "Lalle wannan tabbas mai sihiri ne ƙwararre
(35) "Yana nufi ne ya fitar da ku daga ƙasarku da sihirinsa, to da me za ku yi umarni?"
(36) Suka ce: "Ka dakatar da shi tare da ɗan'uwansa, kuma ka aika manzanni cikin birane su tattaro maka (masu sihiri)
(37) "Su zo maka da duk wani mai sihiri ƙwararre."(38)Sai aka tattara masu sihirin (don su zo) a ƙayyadajjiyar rana sananniya(1)
(39) Aka kuma ce da mutane: "Shin za ku tattaru

(1) Watau ranar bikin idinsu.

لَعَلَّنَا نَتَّبِعُ ٱلسَّحَرَةَ إِن كَانُوا۟ هُمُ ٱلْغَٰلِبِينَ ﴿٤٠﴾ فَلَمَّا جَآءَ ٱلسَّحَرَةُ
قَالُوا۟ لِفِرْعَوْنَ أَئِنَّ لَنَا لَأَجْرًا إِن كُنَّا نَحْنُ ٱلْغَٰلِبِينَ ﴿٤١﴾ قَالَ نَعَمْ
وَإِنَّكُمْ إِذًا لَّمِنَ ٱلْمُقَرَّبِينَ ﴿٤٢﴾ قَالَ لَهُم مُّوسَىٰٓ أَلْقُوا۟ مَآ أَنتُم مُّلْقُونَ
﴿٤٣﴾ فَأَلْقَوْا۟ حِبَالَهُمْ وَعِصِيَّهُمْ وَقَالُوا۟ بِعِزَّةِ فِرْعَوْنَ إِنَّا لَنَحْنُ
ٱلْغَٰلِبُونَ ﴿٤٤﴾ فَأَلْقَىٰ مُوسَىٰ عَصَاهُ فَإِذَا هِىَ تَلْقَفُ مَا يَأْفِكُونَ
﴿٤٥﴾ فَأُلْقِىَ ٱلسَّحَرَةُ سَٰجِدِينَ ﴿٤٦﴾ قَالُوٓا۟ ءَامَنَّا بِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٤٧﴾
رَبِّ مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ﴿٤٨﴾ قَالَ ءَامَنتُمْ لَهُۥ قَبْلَ أَنْ ءَاذَنَ لَكُمْ ۖ إِنَّهُۥ
لَكَبِيرُكُمُ ٱلَّذِى عَلَّمَكُمُ ٱلسِّحْرَ فَلَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ۚ لَأُقَطِّعَنَّ أَيْدِيَكُمْ
وَأَرْجُلَكُم مِّنْ خِلَٰفٍ وَلَأُصَلِّبَنَّكُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٤٩﴾ قَالُوا۟ لَا ضَيْرَ ۖ إِنَّآ
إِلَىٰ رَبِّنَا مُنقَلِبُونَ ﴿٥٠﴾ إِنَّا نَطْمَعُ أَن يَغْفِرَ لَنَا رَبُّنَا خَطَٰيَٰنَآ أَن كُنَّآ
أَوَّلَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٥١﴾ ۞ وَأَوْحَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنْ أَسْرِ بِعِبَادِىٓ إِنَّكُم
مُّتَّبَعُونَ ﴿٥٢﴾ فَأَرْسَلَ فِرْعَوْنُ فِى ٱلْمَدَآئِنِ حَٰشِرِينَ ﴿٥٣﴾ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ
لَشِرْذِمَةٌ قَلِيلُونَ ﴿٥٤﴾ وَإِنَّهُمْ لَنَا لَغَآئِظُونَ ﴿٥٥﴾ وَإِنَّا لَجَمِيعٌ حَٰذِرُونَ
﴿٥٦﴾ فَأَخْرَجْنَٰهُم مِّن جَنَّٰتٍ وَعُيُونٍ ﴿٥٧﴾ وَكُنُوزٍ وَمَقَامٍ كَرِيمٍ ﴿٥٨﴾
كَذَٰلِكَ ۖ وَأَوْرَثْنَٰهَا بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿٥٩﴾ فَأَتْبَعُوهُم مُّشْرِقِينَ ﴿٦٠﴾


(40) "Don mu goyi bayan masu sihiri idan har sun kasance su ne masu galaba?"
(41) Sannan lokacin da masu sihirin suka zo sai suka ce da Fir'auna: "Shin muna da wani lada (da za ka ba mu) in har mun zama mu ne masu galaba?"
(42) (Fir'auna) ya ce: "Na'am, kuma ma idan haka ya faru, to tabbas za ku zama daga makusanta."
(43) (Sai Musa) ya ce da su: "Ku jefa duk abin da za ku jefa."
(44) Sai suka jefa igiyoyinsu da sandunansu suka kuma ce: "Lalle da izzar Fir'auna tabbas mu ne masu galaba."
(45) Sai Musa ya jefa sandarsa, sai ga ta tana lanƙwame duk abin da suke ƙagowa (na sihiri)
(46) Sai aka durƙusar da masu sihirin suna masu sujjada
(47) Suka ce: "Mun yi imani da Ubangijin talikai
(48) "Ubangijin Musa da Haruna."
(49)
(Sai Fir'auna) ya ce: "Yanzu kwa yi imani da shi tun kafin in ba ku izini? Lalle tabbas shi ne babbanku wanda ya koya muku sihiri; to tabbas kuwa kwa sani. Lalle zan yanyanke hannayenku da ƙafafuwanku a tarnaƙe, kuma tabbas zan gicciye ku gaba ɗaya!"
(50) Sai suka ce: "Ai ba damuwa; lalle mu masu komawa ne zuwa ga Ubangijinmu
(51) "Lalle mu muna kwaɗayin Ubangijinmu Ya gafarta mana kurakuranmu saboda zamantowarmu farkon muminai."
(52) Muka kuma yi wa Musa wahayi cewa: "Ka tafi cikin dare tare da bayina, lalle ku za a biyo bayanku."
(53) Sai Fir'auna ya aika zuwa birane don a tattaro (mayaƙa)
(54) (Fir'auna yana cewa): "Lalle waɗannan tabbas 'yan tsirarin jama'a ne
(55) "Kuma haƙiƙa su lalle suna fusata mu
(56) "Lalle kuma mu tabbas gaba ɗayanmu masu kwana cikin shiri ne."
(57) (Allah Ya ce): Sai Muka fitar da su daga gonaki da kuma idandunan ruwa
(58) Da taskoki da kuma mazauni na alfarma
(59) Kamar haka ne Muka gadar da su ga Banu-Isra'ila
(60) Sai suka bi bayansu a lokacin fitowar rana

فَلَمَّا تَرَٰٓءَا ٱلْجَمْعَانِ قَالَ أَصْحَٰبُ مُوسَىٰٓ إِنَّا لَمُدْرَكُونَ ﴿٦١﴾
قَالَ كَلَّآ ۖ إِنَّ مَعِىَ رَبِّى سَيَهْدِينِ ﴿٦٢﴾ فَأَوْحَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنِ
ٱضْرِب بِّعَصَاكَ ٱلْبَحْرَ ۖ فَٱنفَلَقَ فَكَانَ كُلُّ فِرْقٍ كَٱلطَّوْدِ ٱلْعَظِيمِ
﴿٦٣﴾ وَأَزْلَفْنَا ثَمَّ ٱلْءَاخَرِينَ ﴿٦٤﴾ وَأَنجَيْنَا مُوسَىٰ وَمَن مَّعَهُۥٓ أَجْمَعِينَ
﴿٦٥﴾ ثُمَّ أَغْرَقْنَا ٱلْءَاخَرِينَ ﴿٦٦﴾ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً ۖ وَمَا كَانَ
أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٦٧﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٦٨﴾
وَٱتْلُ عَلَيْهِمْ نَبَأَ إِبْرَٰهِيمَ ﴿٦٩﴾ إِذْ قَالَ لِأَبِيهِ وَقَوْمِهِۦ مَا تَعْبُدُونَ
﴿٧٠﴾ قَالُوا۟ نَعْبُدُ أَصْنَامًا فَنَظَلُّ لَهَا عَٰكِفِينَ ﴿٧١﴾ قَالَ هَلْ
يَسْمَعُونَكُمْ إِذْ تَدْعُونَ ﴿٧٢﴾ أَوْ يَنفَعُونَكُمْ أَوْ يَضُرُّونَ ﴿٧٣﴾ قَالُوا۟
بَلْ وَجَدْنَآ ءَابَآءَنَا كَذَٰلِكَ يَفْعَلُونَ ﴿٧٤﴾ قَالَ أَفَرَءَيْتُم مَّا كُنتُمْ
تَعْبُدُونَ ﴿٧٥﴾ أَنتُمْ وَءَابَآؤُكُمُ ٱلْأَقْدَمُونَ ﴿٧٦﴾ فَإِنَّهُمْ عَدُوٌّ لِّىٓ
إِلَّا رَبَّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٧٧﴾ ٱلَّذِى خَلَقَنِى فَهُوَ يَهْدِينِ ﴿٧٨﴾ وَٱلَّذِى هُوَ
يُطْعِمُنِى وَيَسْقِينِ ﴿٧٩﴾ وَإِذَا مَرِضْتُ فَهُوَ يَشْفِينِ ﴿٨٠﴾ وَٱلَّذِى
يُمِيتُنِى ثُمَّ يُحْيِينِ ﴿٨١﴾ وَٱلَّذِىٓ أَطْمَعُ أَن يَغْفِرَ لِى خَطِيٓـَٔتِى
يَوْمَ ٱلدِّينِ ﴿٨٢﴾ رَبِّ هَبْ لِى حُكْمًا وَأَلْحِقْنِى بِٱلصَّٰلِحِينَ ﴿٨٣﴾

(61) To lokacin da jama'ar biyu suka ga juna, sai sahabban Musa suka ce: "Lalle tabbas mu za a cim mana."(62) (Musa) ya ce: "A'a; Ubangijina Yana tare da ni, zai kuwa shiryar da ni (hanyar tsira)."
(63) Sai Muka yi wahayi ga Musa cewa: "Ka bugi kogin da sandarka;" (da ya buge shi) sai ya dare, kowanne yanki sai ya zama kamar ƙaton dutse
(64) Muka kuma kusantar da waɗancan (watau mutanen Fir'auna) zuwa can (kusa da kogin)(65) Muka kuma tserar da Musa da waɗanda suke

(66) Sannan Muka nutsar da sauran mutanen (watau Fir'auna da mutanensa)
(67)Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; kuma yawancinsu ba su zamanto muminai ba
(68) Kuma lalle Ubangijika tabbas Shi Mabuwayi ne, Mai rahama
(69) Kuma ka karanta musu labarin Ibrahimu?
(70) Lokacin da ya ce wa babansa da kuma mutanensa: "Me kuke bauta wa?"
(71) Suka ce: "Muna bauta wa gumaka ne, sai mukan dukufa wajen bautarsu."
(72) (Ibrahimu) ya ce: "Shin suna jin ku kuwa lokacin da kuke kiran su?
(73) "Ko kuwa suna amfanar ku ne, ko suna cutarwa?"
(74) Suka ce: "A'a; mun sami iyayenmu ne suna aikata kamar haka."
(75) (Ibrahimu) ya ce: "Yanzu kun ga abin nan da kuka kasance kuna bautawa
(76) "Ku da iyayenku da suka gabata
(77) "To lalle su abokan gabata ne sai fa Ubangijin talikai
(78) "Wanda Ya halicce ni, to Shi ne Yake shiryar da ni
(79) "Kuma wanda Shi ne Yake ciyar da ni kuma Yake shayar da ni
(80) "Idan kuma na yi rashin lafiya, to Shi ne zai warkar da ni
(81) "Kuma wanda zai kashe ni sannan Ya (sake) raya ni
(82) "Wanda kuma nake kwaɗayin Ya gafarta min kurakuraina ranar sakamako
(83) "Ubangijina Ka hore min ilimi, kuma Ka haɗa ni da (bayinka) na gari

26 Sura Shu'ara Izifi 38 Juzu'i 19



(84) “Kuma Ka sanya min abin kyakkyawan ambato cikin ‘yan baya (85) “Kuma Ka sanya ni cikin magada Aljannar ni’ima (86) “Kuma Ka gafarta wa babana, lalle shi ya zamo cikin ɓatattu.[1] (87) “Kada kuma Ka kunyata ni ranar da za a tashe su(88) “Ranar da dukiya da ‘ya’yaye ba sa amfani (89) “Sai dai wanda ya zo wa Allah da lafiyayyar zuciya.” (90) Aka kuma kusantar da Aljanna ga masu taƙawa (91) Kuma aka bayyanar da (wutar) Jahima ga ɓatattu (92) Aka kuma ce da su: “Ina abubuwan da kuka kasance kuna bauta wa? (93) “Waɗanda ba Allah ba? Shin za su taimake ku, ko za su taimaki kansu?” (94) Sai aka kikkifa su cikinta (wutar) su da ɓatattu (95) Da kuma rundunar Iblis gaba ɗaya (96) Sai suka ce, alhali suna jayayya da juna a cikinta: (97) “Mun rantse da Allah tabbas mun kasance (a duniya) cikin ɓata bayyananne (98) “Lokacin da muke daidaita ku da Ubangijin talikai[2] (99) “Ba kuwa waɗanda suka ɓatar da mu sai manyan masu laifuka (100) “To a (yau) ba mu da wasu masu ceto (101) “Ba kuma wani aboki na ƙut-da-ƙut (102) “To ina ma da za mu samu damar komawa, sai mu zamanto daga muminai!” (103) Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; kuma yawancinsu, ba su zamanto muminai ba (104) Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi ne Mabuwayi Mai jin ƙai (105) Mutanen Nuhu sun ƙaryata mazanni[3] (106) Lokacin da ɗan’uwansu Nuhu ya ce da su: “Yanzu ba za ku kiyaye dokokin Allah ba?(107) “Lalle ni Manzo ne amintacce a gare ku (108) “To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni
(109) “Ba na kuma tambayar ku wani lada a game da shi (isar da manzancin). Ladana yana wajen Ubangijin talikai kawai (110) “To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni.” (111) Suka ce: “Yanzu ma yi imani da kai alhali ƙasƙantattu ne mabiyanka?”

(1) Ya yi masa wannan addu’a ne tun gabanin a hana shi, kamar yadda ya zo a cikin Suratut Tauba, aya ta 114.

(2) Watau wajen soyayya da bauta.

(3) Domin qaryata Annabi Nuhu ( ) daidai yake da qaryata dukkan manzannin Allah, domin saqo iri xaya suke xauke da shi.

قَالَ وَمَا عِلْمِي بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١١٢﴾ إِنْ حِسَابُهُمْ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّى ۖ
لَوْ تَشْعُرُونَ ﴿١١٣﴾ وَمَآ أَنَا۠ بِطَارِدِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١١٤﴾ إِنْ أَنَا۠ إِلَّا نَذِيرٌ مُّبِينٌ
﴿١١٥﴾ قَالُوا۟ لَئِن لَّمْ تَنتَهِ يَٰنُوحُ لَتَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمَرْجُومِينَ ﴿١١٦﴾ قَالَ
رَبِّ إِنَّ قَوْمِى كَذَّبُونِ ﴿١١٧﴾ فَٱفْتَحْ بَيْنِى وَبَيْنَهُمْ فَتْحًا وَنَجِّنِى وَمَن
مَّعِىَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١١٨﴾ فَأَنجَيْنَٰهُ وَمَن مَّعَهُۥ فِى ٱلْفُلْكِ ٱلْمَشْحُونِ
﴿١١٩﴾ ثُمَّ أَغْرَقْنَا بَعْدُ ٱلْبَاقِينَ ﴿١٢٠﴾ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً ۖ وَمَا كَانَ
أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٢١﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٢٢﴾ كَذَّبَتْ
عَادٌ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿١٢٣﴾ إِذْ قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ هُودٌ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿١٢٤﴾ إِنِّى لَكُمْ
رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿١٢٥﴾ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١٢٦﴾ وَمَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ
مِنْ أَجْرٍ ۖ إِنْ أَجْرِىَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٢٧﴾ أَتَبْنُونَ بِكُلِّ رِيعٍ
ءَايَةً تَعْبَثُونَ ﴿١٢٨﴾ وَتَتَّخِذُونَ مَصَانِعَ لَعَلَّكُمْ تَخْلُدُونَ ﴿١٢٩﴾
وَإِذَا بَطَشْتُم بَطَشْتُمْ جَبَّارِينَ ﴿١٣٠﴾ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١٣١﴾
وَٱتَّقُوا۟ ٱلَّذِىٓ أَمَدَّكُم بِمَا تَعْلَمُونَ ﴿١٣٢﴾ أَمَدَّكُم بِأَنْعَٰمٍ وَبَنِينَ
﴿١٣٣﴾ وَجَنَّٰتٍ وَعُيُونٍ ﴿١٣٤﴾ إِنِّىٓ أَخَافُ عَلَيْكُمْ عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ
﴿١٣٥﴾ قَالُوا۟ سَوَآءٌ عَلَيْنَآ أَوَعَظْتَ أَمْ لَمْ تَكُن مِّنَ ٱلْوَٰعِظِينَ ﴿١٣٦﴾

(112) Ya ce: "Ba ni da sani game da abin da suka zamanto suna aikata
(113) "Hisabinsu kawai yana wajen Ubangijina ne; da za ku gane
(114) "Ni kuma ba mai korar muminai ba ne
(115) "Ni kawai mai gargaɗi ne mai bayyanawa."
(116) Suka ce: "Ya Nuhu, mun rantse idan ba ka daina (faɗar abin da kake faɗa) ba, tabbas za ka zamanto daga cikin jefaffu!"
(117) Ya ce: "Ya Ubangijina,
(118) "Ka yi hukunci tsakanina da su, kuma Ka tserar da ni tare da muminan da suke tare da ni."
(119) Sai Muka tserar da shi da waɗanda suke tare da shi a cikin jirgin ruwan da ke maƙare (da mutane da dabbobi) (120) Sannan bayan haka Muka nutsar da sauran (121) Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; kuma yawancinsu ba su zamanto muminai ba (122) Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi ne Mabuwayi, Mai jin ƙai (123) Adawa (ma) sun ƙaryata manzanni(1) (124)Lokacin da ɗan'uwansu Hudu ya ce da su: "Yanzu ba kwa riƙa kiyaye dokokin (Allah) ba?(125)"Lalle ni Manzo ne amintacce gare ku (126) "To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni (127) "Kuma ba na tambayar ku wani lada game da shi (isar da manzancin); ladana yana wajen Ubangijin talikai kawai (128) "Yanzu kwa riƙa yin dogayen gine-gine a kan tuddai kuna sharholiya? (129) "Kuma ku riƙa gina ganuwoyi da maka-makan gidaje kamar za ku dawwama? (130) "Idan kuma kuka yi damƙa sai kukan yi damƙa da tsanani (131)"To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni (132)"Kuma ku kiyaye dokokin (Allah) wanda Ya ni'imta ku da abin da kuka sani (133) "Ya ni'imta ku da dabbobin ni'ima da 'ya'ya(134) "Da kuma gonakai da idanuwan ruwa(135) "Lalle ni ina jiye muku tsoron azabar wani yini mai girma."(136) Suka ce: "Mu duk ɗaya ne a wajenmu; ko ka yi wa'azi ko kuwa kada ka zamanto daga masu wa'azi

(1) Domin qaryata Annabi Hudu ( ) daidai yake da qaryata duk manzannin Allah, saboda saqo iri xaya suke xauke da shi.

إِنْ هَٰذَآ إِلَّا خُلُقُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿١٣٧﴾ وَمَا نَحْنُ بِمُعَذَّبِينَ ﴿١٣٨﴾ فَكَذَّبُوهُ
فَأَهْلَكْنَٰهُمْ ۗ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً ۖ وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٣٩﴾
وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٤٠﴾ كَذَّبَتْ ثَمُودُ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿١٤١﴾ إِذْ
قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ صَٰلِحٌ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿١٤٢﴾ إِنِّى لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿١٤٣﴾
فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١٤٤﴾ وَمَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ ۖ إِنْ أَجْرِىَ
إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٤٥﴾ أَتُتْرَكُونَ فِى مَا هَٰهُنَآ ءَامِنِينَ ﴿١٤٦﴾
فِى جَنَّٰتٍ وَعُيُونٍ ﴿١٤٧﴾ وَزُرُوعٍ وَنَخْلٍ طَلْعُهَا هَضِيمٌ ﴿١٤٨﴾
وَتَنْحِتُونَ مِنَ ٱلْجِبَالِ بُيُوتًا فَٰرِهِينَ ﴿١٤٩﴾ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ
﴿١٥٠﴾ وَلَا تُطِيعُوٓا۟ أَمْرَ ٱلْمُسْرِفِينَ ﴿١٥١﴾ ٱلَّذِينَ يُفْسِدُونَ فِى ٱلْأَرْضِ
وَلَا يُصْلِحُونَ ﴿١٥٢﴾ قَالُوٓا۟ إِنَّمَآ أَنتَ مِنَ ٱلْمُسَحَّرِينَ ﴿١٥٣﴾ مَآ أَنتَ
إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُنَا فَأْتِ بِـَٔايَةٍ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿١٥٤﴾ قَالَ
هَٰذِهِۦ نَاقَةٌ لَّهَا شِرْبٌ وَلَكُمْ شِرْبُ يَوْمٍ مَّعْلُومٍ ﴿١٥٥﴾ وَلَا تَمَسُّوهَا
بِسُوٓءٍ فَيَأْخُذَكُمْ عَذَابُ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿١٥٦﴾ فَعَقَرُوهَا فَأَصْبَحُوا۟
نَٰدِمِينَ ﴿١٥٧﴾ فَأَخَذَهُمُ ٱلْعَذَابُ ۗ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً ۖ وَمَا كَانَ
أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٥٨﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٥٩﴾

(137) "Wannan ba wani abu ba ne in ban da halayyar mutanen farko
(138) "Mu kuma ba waɗanda za a yi wa azaba ba ne."
(139) Sai suka ƙaryata shi, sannan Muka hallaka su. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; kuma yawancinsu ba su zamanto muminai ba
(140) Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi ne Mabuwayi, Mai jin ƙai
(141) Samudawa sun ƙaryata manzanni[1]
(142) Lokacin da ɗan'uwansu Salihu ya ce da su: "Yanzu ba kwa yi taƙawa ba?
(143) "Lalle ni Manzo ne amintacce gare ku
(144) "To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni
(145) "Kuma ba na tambayar ku wani lada game da shi (isar da manzancin); ladana yana wajen Ubangijin talikai kawai
(146) "Yanzu (zatonku) za a bar ku ne cikin abin da yake a nan (duniya) cikin kwanciyar hankali?
(147) "(Watau) a cikin gonaki da idandunan ruwa?
(148) "Da shuke-shuke da dabinai masu taushin 'ya'ya?
(149) "Kuma kuna fafe duwatsu kuna yin gidaje kuna masu nuna ƙwarewa?
(150) "To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni
(151) "Kada kuma ku bi umarnin maɓarnata
(152) "Waɗanda suke ɓarna a bayan ƙasa, kuma ba sa gyara."
(153) Suka ce: "Lalle kai kana daga waɗanda aka sihirce ne kawai
(154) "Kai ba kowa ba ne sai mutum kamarmu, to ka zo mana da aya idan ka kasance daga masu gaskiya."
(155) (Salihu) ya ce: "Wannan taguwa ce[2], tana da (ranar) shanta ku ma kuna da rana sananniya ta shanku
(156) "Kada kuwa ku shafe ta da mugun abu, sai azabar wani yini mai girma ta kama ku."
(157) Sai suka soke ta, sai kuwa suka wayi gari suna masu nadama
(158) Sai azaba ta kama su. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; kuma yawancinsu ba su zamanto muminai ba
(159) Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi ne Mabuwayi, Mai jin ƙai

(1) Domin qaryata Annabi Salihu ( ) daidai yake da qaryata duk manzannin Allah, saboda saqo iri xaya suke xauke da shi.
(2) Watau a matsayin mu'ujiza ga Annabi Salihu ( ).

كَذَّبَتْ قَوْمُ لُوطٍ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿١٦٠﴾ إِذْ قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ لُوطٌ أَلَا تَتَّقُونَ
﴿١٦١﴾ إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿١٦٢﴾ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١٦٣﴾ وَمَآ
أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ ۖ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٦٤﴾
أَتَأْتُونَ ٱلذُّكْرَانَ مِنَ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٦٥﴾ وَتَذَرُونَ مَا خَلَقَ لَكُمْ رَبُّكُم
مِّنْ أَزْوَٰجِكُم ۚ بَلْ أَنتُمْ قَوْمٌ عَادُونَ ﴿١٦٦﴾ قَالُوا۟ لَئِن لَّمْ تَنتَهِ يَٰلُوطُ
لَتَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُخْرَجِينَ ﴿١٦٧﴾ قَالَ إِنِّي لِعَمَلِكُم مِّنَ ٱلْقَالِينَ ﴿١٦٨﴾
رَبِّ نَجِّنِي وَأَهْلِي مِمَّا يَعْمَلُونَ ﴿١٦٩﴾ فَنَجَّيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥٓ أَجْمَعِينَ ﴿١٧٠﴾
إِلَّا عَجُوزًا فِي ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿١٧١﴾ ثُمَّ دَمَّرْنَا ٱلْـَٔاخَرِينَ ﴿١٧٢﴾ وَأَمْطَرْنَا عَلَيْهِم
مَّطَرًا ۖ فَسَآءَ مَطَرُ ٱلْمُنذَرِينَ ﴿١٧٣﴾ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَءَايَةً ۖ وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم
مُّؤْمِنِينَ ﴿١٧٤﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٧٥﴾ كَذَّبَ أَصْحَٰبُ
لْـَٔيْكَةِ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿١٧٦﴾ إِذْ قَالَ لَهُمْ شُعَيْبٌ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿١٧٧﴾ إِنِّي لَكُمْ
رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿١٧٨﴾ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١٧٩﴾ وَمَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ
مِنْ أَجْرٍ ۖ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٨٠﴾ ۞ أَوْفُوا۟ ٱلْكَيْلَ وَلَا
تَكُونُوا۟ مِنَ ٱلْمُخْسِرِينَ ﴿١٨١﴾ وَزِنُوا۟ بِٱلْقِسْطَاسِ ٱلْمُسْتَقِيمِ ﴿١٨٢﴾
وَلَا تَبْخَسُوا۟ ٱلنَّاسَ أَشْيَآءَهُمْ وَلَا تَعْثَوْا۟ فِي ٱلْأَرْضِ مُفْسِدِينَ ﴿١٨٣﴾

(160) Mutanen Ludu sun ƙaryata manzanni
(161) Lokacin da ɗan'uwansu Ludu ya ce da su: "Yanzu ba kwa kiyaye dokokin Allah ba?
(162) "Lalle ni Manzo ne amintacce gare ku
(163) "To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni
(164) "Kuma ba na tambayar ku wani lada game da shi (isar da manzancin); ladana yana wajen Ubangijin talikai kawai
(165) "Yanzu kwa riƙa zaike wa maza daga halittu?
(166) "Kuma ku bar abin da Ubangijinku Ya halitta na matanku dominku? A'a, ku dai mutane ne masu ƙetare iyaka."
(167) Suka ce: "Tabbas Ludu idan ba ka bar (faɗar abin da kake faɗa ba) haƙiƙa za ka kasance daga korarru (daga garin nan)."
(168) (Ludu) ya ce: "Lalle ni ina cikin masu ƙyamar aikin nan naku
(169) "Ya Ubangijina, Ka tserar da ni da iyalina daga (sakamakon) abin da suke aikatawa."
(170) Sai Muka tserar da shi da iyalinsa gaba ɗaya
(171) Sai fa wata tsohuwa (watau matarsa) da ta (kasance tana) cikin hallakakku
(172) Sannan Muka hallaka sauran
(173) Muka kuma saukar musu da ruwa na azaba; to ruwan azabar waɗanda aka yi wa gargaɗi ya munana
(174) Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; yawancinsu kuwa ba su zamanto muminai ba
(175) Kuma lalle Ubangiijnka tabbas Shi ne Mabuwayi, Mai jin ƙai
(176) Mutanen kurmi sun ƙaryata manzanni
(177) Lokacin da Shu'aibu ya ce da su: "Yanzu ba kwa kiyaye dokokin (Allah) ba?
(178) "Lalle ni Manzo ne amintacce gare ku
(179) "To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni
(180) "Kuma ba na tambayar ku wani lada game da shi (isar da manzancin); ladana yana wajen Ubangijin talikai kawai
(181) "Ku cika mudu kada kuma ku zamanto daga masu tauye (shi)
(182) "Kuma ku riƙa yin awon nauyi da ma'auni na adalci
(183) "Kada kuma ku tauye wa mutane kayayyakinsu, kuma kada ku yawaita ɓarna a bayan ƙasa

وَٱتَّقُوا۟ ٱلَّذِى خَلَقَكُمْ وَٱلْجِبِلَّةَ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿١٨٤﴾ قَالُوٓا۟ إِنَّمَآ أَنتَ مِنَ
ٱلْمُسَحَّرِينَ ﴿١٨٥﴾ وَمَآ أَنتَ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُنَا وَإِن نَّظُنُّكَ لَمِنَ
ٱلْكَٰذِبِينَ ﴿١٨٦﴾ فَأَسْقِطْ عَلَيْنَا كِسَفًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ إِن كُنتَ
مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿١٨٧﴾ قَالَ رَبِّىٓ أَعْلَمُ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿١٨٨﴾ فَكَذَّبُوهُ
فَأَخَذَهُمْ عَذَابُ يَوْمِ ٱلظُّلَّةِ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿١٨٩﴾
إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً ۖ وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٩٠﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ
لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٩١﴾ وَإِنَّهُۥ لَتَنزِيلُ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٩٢﴾ نَزَلَ بِهِ
ٱلرُّوحُ ٱلْأَمِينُ ﴿١٩٣﴾ عَلَىٰ قَلْبِكَ لِتَكُونَ مِنَ ٱلْمُنذِرِينَ ﴿١٩٤﴾ بِلِسَانٍ
عَرَبِىٍّ مُّبِينٍ ﴿١٩٥﴾ وَإِنَّهُۥ لَفِى زُبُرِ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿١٩٦﴾ أَوَلَمْ يَكُن لَّهُمْ ءَايَةً
أَن يَعْلَمَهُۥ عُلَمَٰٓؤُا۟ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿١٩٧﴾ وَلَوْ نَزَّلْنَٰهُ عَلَىٰ بَعْضِ ٱلْأَعْجَمِينَ
﴿١٩٨﴾ فَقَرَأَهُۥ عَلَيْهِم مَّا كَانُوا۟ بِهِۦ مُؤْمِنِينَ ﴿١٩٩﴾ كَذَٰلِكَ سَلَكْنَٰهُ
فِى قُلُوبِ ٱلْمُجْرِمِينَ ﴿٢٠٠﴾ لَا يُؤْمِنُونَ بِهِۦ حَتَّىٰ يَرَوُا۟ ٱلْعَذَابَ
ٱلْأَلِيمَ ﴿٢٠١﴾ فَيَأْتِيَهُم بَغْتَةً وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿٢٠٢﴾ فَيَقُولُوا۟
هَلْ نَحْنُ مُنظَرُونَ ﴿٢٠٣﴾ أَفَبِعَذَابِنَا يَسْتَعْجِلُونَ ﴿٢٠٤﴾ أَفَرَءَيْتَ
إِن مَّتَّعْنَٰهُمْ سِنِينَ ﴿٢٠٥﴾ ثُمَّ جَآءَهُم مَّا كَانُوا۟ يُوعَدُونَ ﴿٢٠٦﴾

(184) "Kuma ku kiyaye dokokin (Allah) wanda Ya halicce ku da kuma al'ummu na farko."
(185) Suka ce: "Kai dai kana daga waɗanda aka sihirce ne kawai
(186) "Kuma kai ba kowa ba ne sai mutum kamarmu, kuma ma lalle muna zaton kana daga maƙaryata!
(187) "Sai ka jeho mana da yankuna (na azaba) daga sama in ka kasance daga masu gaskiya!"
(188) (Shu'aibu) Ya ce: "Ubangijina Ya fi kowa sanin abin da kuke aikatawa."

(189) Sai suka ƙaryata shi, sannan sai azabar yinin girgije (na wuta) ta kama su. Lalle ta kasance azabar wani yini ne mai girma
(190) Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; sai dai kuma yawancinsu ba su kasance muminai ba
(191) Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi ne Mabuwayi, Mai rahama
(192) Kuma lalle shi (Alƙur'ani) saukarwa ce ta Ubangijin talikai
(193) Ruhi amintacce (watau Jibrilu) ne ya sauko da shi
(194) A bisa zuciyarka don ka zamanto daga masu gargaɗi
(195) (Ya saukar da shi) da harshen Larabci mabayyani
(196) Kuma lalle shi yana daga cikin littattafan farko
(197) Yanzu bai ishe su aya ba cewa, malaman Banu- Isra'ila sun san shi?
(198) Da kuwa Mun saukar da shi ga wani wanda ba Balarabe ba
(199) Sannan ya karanta musu shi, to da ba za su yi imani da shi ba
(200) Kamar haka ne Muka shigar da shi (ƙaryata Annabi) cikin zukatan manyan masu laifi
(201) Ba za su yi imani da shi ba har sai sun ga azaba mai raɗaɗi
(202) Sannan (azabar) za ta zo musu ba zato ba tsammani, ba tare da suna sane ba
(203) Sai su ce: "Yanzu za a saurara mana?"
(204) Yanzu azabarmu suke neman gaggautowa?
(205) Ka ba Ni labari idan Muka jiyar da su daɗi na tsawon shekaru
(206) Sannan kuma abin da ake yi musu alkawarin narko da shi ya zo musu

مَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يُمَتَّعُونَ ﴿٢٠٧﴾ وَمَآ أَهۡلَكۡنَا مِن قَرۡيَةٍ إِلَّا
لَهَا مُنذِرُونَ ﴿٢٠٨﴾ ذِكۡرَىٰ وَمَا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ﴿٢٠٩﴾ وَمَا تَنَزَّلَتۡ بِهِ
ٱلشَّيَٰطِينُ ﴿٢١٠﴾ وَمَا يَنۢبَغِي لَهُمۡ وَمَا يَسۡتَطِيعُونَ ﴿٢١١﴾ إِنَّهُمۡ عَنِ
ٱلسَّمۡعِ لَمَعۡزُولُونَ ﴿٢١٢﴾ فَلَا تَدۡعُ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ فَتَكُونَ
مِنَ ٱلۡمُعَذَّبِينَ ﴿٢١٣﴾ وَأَنذِرۡ عَشِيرَتَكَ ٱلۡأَقۡرَبِينَ ﴿٢١٤﴾ وَٱخۡفِضۡ
جَنَاحَكَ لِمَنِ ٱتَّبَعَكَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿٢١٥﴾ فَإِنۡ عَصَوۡكَ فَقُلۡ إِنِّي
بَرِيٓءٞ مِّمَّا تَعۡمَلُونَ ﴿٢١٦﴾ وَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱلۡعَزِيزِ ٱلرَّحِيمِ ﴿٢١٧﴾ ٱلَّذِي
يَرَىٰكَ حِينَ تَقُومُ ﴿٢١٨﴾ وَتَقَلُّبَكَ فِي ٱلسَّٰجِدِينَ ﴿٢١٩﴾ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ
ٱلۡعَلِيمُ ﴿٢٢٠﴾ هَلۡ أُنَبِّئُكُمۡ عَلَىٰ مَن تَنَزَّلُ ٱلشَّيَٰطِينُ ﴿٢٢١﴾ تَنَزَّلُ عَلَىٰ
كُلِّ أَفَّاكٍ أَثِيمٖ ﴿٢٢٢﴾ يُلۡقُونَ ٱلسَّمۡعَ وَأَكۡثَرُهُمۡ كَٰذِبُونَ ﴿٢٢٣﴾
وَٱلشُّعَرَآءُ يَتَّبِعُهُمُ ٱلۡغَاوُۥنَ ﴿٢٢٤﴾ أَلَمۡ تَرَ أَنَّهُمۡ فِي كُلِّ وَادٖ
يَهِيمُونَ ﴿٢٢٥﴾ وَأَنَّهُمۡ يَقُولُونَ مَا لَا يَفۡعَلُونَ ﴿٢٢٦﴾ إِلَّا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَذَكَرُواْ ٱللَّهَ كَثِيرٗا وَٱنتَصَرُواْ مِنۢ
بَعۡدِ مَا ظُلِمُواْۚ وَسَيَعۡلَمُ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓاْ أَيَّ مُنقَلَبٖ يَنقَلِبُونَ ﴿٢٢٧﴾

سُورَةُ النَّمۡلِ

(207) Abin da ake jiyar da su dadi a da ba zai amfana musu komai ba
(208) Ba Mu taba hallaka wata al'umma ba face sai ta samu masu yi mata gargadi
(209) (Wannan) tunatarwa ce (gare su), ba Mu kuwa kasance azzalumai ba
(210) Kuma shaidanu ba su sauko da shi ba
(211) Kuma bai kamace su ba, ba kuma za su iya ba
(212) Lalle su ababen kangewa ne daga jin (wahayi)
(213) To kada ka bauta wa wani tare da Allah, sai ka zamanto daga wadanda za a yi wa azaba

(214) Kuma ka gargadi danginka mafiya kusanci
(215) Ka kuma tausasa ga wanda ya bi ka daga muminai(216) To idan suka saba maka sai ka ce: "Ni lalle ba ruwana da abin da kuke aikatawa."
(217) Ka kuma dogara ga Mabuwayi, Mai rahama
(218) Wanda Yake ganin ka yayin da kake tashi (don yin salla)
(219) Da kuma (yayin) jujjuyawarka cikin masu sujjada(1)
(220) Hakika Shi Mai ji ne, Masani
(221) Shin ba Na ba ku labari ba game da wanda shedanu suke saukar masa?
(222) Suna sauka ne a kan duk wani makaryaci mai yawan laifi
(223) Suna jefa wa (bokaye) abin da suka sato jinsa, yawancinsu kuwa makaryata ne
(224) Mawaka kuwa batattu ne suke bin su
(225) Ba ka ga cewa su kutsawa suke yi cikin kowanne kwari ba(2)?
(226) Lalle kuma suna fadar abin da ba sa aikatawa
(227) Sai dai wadanda suka yi imani kuma suka yi aiki nagari, kuma suka ambaci Allah da yawa, suka kuma yi sakayya bayan an zalunce su(3). Wadanda suka yi zalunci kuwa ba da dadewa ba za su san kowace makomar za su koma

(1) Watau masallata a sallar jam'i.

(2) Watau suna kutsawa cikin kowane saqo-saqo na waqe-waqe, wani lokaci ta hanyar yabo, wani lokaci kuma ya hanyar zambo ko alfahari, su faxi qarya da gaskiya.

(3) Watau mawaqan Musulmi waxanda suke mayar da martani a kan mawaqan kafirai masu sukan Musulunci.

Sura Namli

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

طسٓ تِلْكَ ءَايَٰتُ ٱلْقُرْءَانِ وَكِتَابٍ مُّبِينٍ ﴿١﴾ هُدًى وَبُشْرَىٰ
لِلْمُؤْمِنِينَ ﴿٢﴾ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤْتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُم
بِٱلْءَاخِرَةِ هُمْ يُوقِنُونَ ﴿٣﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِٱلْءَاخِرَةِ زَيَّنَّا لَهُمْ
أَعْمَٰلَهُمْ فَهُمْ يَعْمَهُونَ ﴿٤﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَهُمْ سُوٓءُ ٱلْعَذَابِ
وَهُمْ فِى ٱلْءَاخِرَةِ هُمُ ٱلْأَخْسَرُونَ ﴿٥﴾ وَإِنَّكَ لَتُلَقَّى ٱلْقُرْءَانَ مِن
لَّدُنْ حَكِيمٍ عَلِيمٍ ﴿٦﴾ إِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِأَهْلِهِۦٓ إِنِّىٓ ءَانَسْتُ نَارًا سَـَٔاتِيكُم
مِّنْهَا بِخَبَرٍ أَوْ ءَاتِيكُم بِشِهَابٍ قَبَسٍ لَّعَلَّكُمْ تَصْطَلُونَ ﴿٧﴾ فَلَمَّا جَآءَهَا
نُودِىَ أَنۢ بُورِكَ مَن فِى ٱلنَّارِ وَمَنْ حَوْلَهَا وَسُبْحَٰنَ ٱللَّهِ رَبِّ
ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٨﴾ يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّهُۥٓ أَنَا ٱللَّهُ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٩﴾ وَأَلْقِ عَصَاكَ
فَلَمَّا رَءَاهَا تَهْتَزُّ كَأَنَّهَا جَآنٌّ وَلَّىٰ مُدْبِرًا وَلَمْ يُعَقِّبْ يَٰمُوسَىٰ لَا تَخَفْ
إِنِّى لَا يَخَافُ لَدَىَّ ٱلْمُرْسَلُونَ ﴿١٠﴾ إِلَّا مَن ظَلَمَ ثُمَّ بَدَّلَ حُسْنًۢا بَعْدَ
سُوٓءٍ فَإِنِّى غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١١﴾ وَأَدْخِلْ يَدَكَ فِى جَيْبِكَ تَخْرُجْ بَيْضَآءَ مِنْ
غَيْرِ سُوٓءٍ ۖ فِى تِسْعِ ءَايَٰتٍ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَقَوْمِهِۦٓ ۚ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ قَوْمًا فَٰسِقِينَ
﴿١٢﴾ فَلَمَّا جَآءَتْهُمْ ءَايَٰتُنَا مُبْصِرَةً قَالُوا۟ هَٰذَا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿١٣﴾

(1) DA SIN[1]. Wadannan ayoyin Alkur'ani ne kuma Littafi mabayyani
(2) (Kuma) shiriya da albishir ne ga muminai
(3) Wadanda suke tsai da salla, suke kuma ba da zakka suna masu sakankancewa da ranar lahira
(4) Lalle wadanda ba sa imani da ranar lahira Mun kawata musu ayyukansu, don haka suke dimuwa
(5) Wadannan su ne wadanda suke da mummunar azaba, kuma su ne suka fi hasara a lahira
(6) Lalle kuma kai tabbas ana yi maka wahayin Alkur'ani ne daga wajen (Allah) Mai hikima, Masani
(7) Ka tuna lokacin da Musa ya ce da iyalinsa: "Lalle ni na hango wata wuta, to (zan je) in zo muku da labari, ko kuma in zo muku da dosanen garwashi don ku ji dumi."
(8) To lokacin da ya zo mata (wutar) sai aka kira shi cewa, an tsarkake wanda yake cikin wutar da wadanda suke daura da ita (wato mala'iku), kuma tsarki ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai
(9) Ya Musa, lalle lamarin dai, Ni ne Allah Mabuwayi, Mai hikima
(10) Kuma ka jefar da sandarka. To lokacin da ya gan ta tana jujjuyawa kamar macijiya, sai ya juya da baya a guje bai dawo ba. (Allah ya ce): Ya Musa, kada ka ji tsoro, lalle Ni manzanni ba sa jin tsoro a wurina
(11) Sai dai wanda ya zalunci (kansa), sannan ya musanya kyakkyawa bayan mummuna, to lalle Ni Mai gafara ne, Mai jin kai
(12) Kuma ka saka hannunka cikin wuyan rigarka, zai fito fari fat ba na cuta ba; (wannan aya ce) daga cikin ayoyi tara zuwa ga Fir'auna da mutanensa. Lalle su sun kasance mutane ne fasikai
(13) To lokacin da ayoyinmu wadanda suke a sarari suka zo musu, sai suka ce: "Wannan sihiri ne mabayyani."

(1) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8.

وَجَحَدُوا۟ بِهَا وَٱسْتَيْقَنَتْهَآ أَنفُسُهُمْ ظُلْمًا وَعُلُوًّا ۚ فَٱنظُرْ كَيْفَ
كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿١٤﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا دَاوُۥدَ وَسُلَيْمَٰنَ عِلْمًا ۖ
وَقَالَا ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِى فَضَّلَنَا عَلَىٰ كَثِيرٍ مِّنْ عِبَادِهِ ٱلْمُؤْمِنِينَ
﴿١٥﴾ وَوَرِثَ سُلَيْمَٰنُ دَاوُۥدَ ۖ وَقَالَ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ عُلِّمْنَا مَنطِقَ
ٱلطَّيْرِ وَأُوتِينَا مِن كُلِّ شَىْءٍ ۖ إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ ٱلْفَضْلُ ٱلْمُبِينُ ﴿١٦﴾
وَحُشِرَ لِسُلَيْمَٰنَ جُنُودُهُۥ مِنَ ٱلْجِنِّ وَٱلْإِنسِ وَٱلطَّيْرِ فَهُمْ
يُوزَعُونَ ﴿١٧﴾ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَتَوْا۟ عَلَىٰ وَادِ ٱلنَّمْلِ قَالَتْ نَمْلَةٌ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلنَّمْلُ ٱدْخُلُوا۟ مَسَٰكِنَكُمْ لَا يَحْطِمَنَّكُمْ سُلَيْمَٰنُ وَجُنُودُهُۥ وَهُمْ
لَا يَشْعُرُونَ ﴿١٨﴾ فَتَبَسَّمَ ضَاحِكًا مِّن قَوْلِهَا وَقَالَ رَبِّ أَوْزِعْنِىٓ
أَنْ أَشْكُرَ نِعْمَتَكَ ٱلَّتِىٓ أَنْعَمْتَ عَلَىَّ وَعَلَىٰ وَٰلِدَىَّ وَأَنْ أَعْمَلَ
صَٰلِحًا تَرْضَىٰهُ وَأَدْخِلْنِى بِرَحْمَتِكَ فِى عِبَادِكَ ٱلصَّٰلِحِينَ
﴿١٩﴾ وَتَفَقَّدَ ٱلطَّيْرَ فَقَالَ مَا لِىَ لَآ أَرَى ٱلْهُدْهُدَ أَمْ كَانَ
مِنَ ٱلْغَآئِبِينَ ﴿٢٠﴾ لَأُعَذِّبَنَّهُۥ عَذَابًا شَدِيدًا أَوْ لَأَا۟ذْبَحَنَّهُۥٓ
أَوْ لَيَأْتِيَنِّى بِسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿٢١﴾ فَمَكَثَ غَيْرَ بَعِيدٍ فَقَالَ
أَحَطتُ بِمَا لَمْ تُحِطْ بِهِۦ وَجِئْتُكَ مِن سَبَإٍۭ بِنَبَإٍ يَقِينٍ ﴿٢٢﴾

(14) Suka kuma musanta su don zalunci da girman kai, alhali kuwa zukatansu sun sakankance da su[1]. To sai ka duba ka ga yadda ƙarshen maɓarnata ya kasance
(15) Haƙiƙa kuma Mun bai wa Dawuda da Sulaimana ilimi; suka kuma ce: "Godiya ta tabbata ga Allah wanda Ya fifita mu a kan masu yawa daga bayinsa muminai."
(16) Sulaimanu kuma ya gaji Dawuda[2]; ya kuma ce: "Ya ku waɗannan mutane, (watau Yahudawa), an sanar da mu zancen tsuntsaye, kuma an ba mu daga kowane abu (na tafiyar da mulki); lalle wannan tabbas ita ce bayyananniyar falala."
(17) Aka kuma tattara wa Sulaimanu rundunoninsa na aljannu da mutane da kuma tsuntsaye, sai aka rika turo su sahu-sahu
(18) Har dai zuwa lokacin da suka iso kwarin tururuwa, sai wata tururuwa ta ce: "Ya ku waɗannan taron tururuwa, ku shige gidajenku kada Sulaimanu da rundunoninsa su tattake ku alhali kuwa ba da saninsu ba."
(19) Sai ya yi murmushi yana mai dariya saboda maganarta, ya kuma ce: "Ubangijina Ka kimsa min yadda zan gode wa ni'imar da Ka yi min ni da mahaifana, da kuma yadda zan yi aiki na gari wanda za Ka yarda da shi, kuma Ka shigar da ni don rahamarka cikin bayinka na gari."
(20) Kuma ya bincika tsuntsaye, sai ya ce: "Me ya sa ba na ganin Alhudahuda, ko kuwa yana cikin waɗanda ba sa nan ne?
(21) "Na rantse zan yi masa azaba mai tsanani, ko kuma tabbas zan yanka shi, ko kuma lalle ya zo min da hujja bayyananna."
(22) Sai ko ba da daɗewa ba ya dawo, sannan (bayan an tambaye shi) ya ce: "Ni fa na gano abin da ba ka sani ba, na kuma zo maka da tabbataccen labari daga birnin Saba'u

(1) Watau a zukatansu sun san gaskiya ce, su kuma a kan qarya suke, amma son zuciya ya hana su su sallama.

(2) Watau gadon ilimi da annabta da Allah ya ba shi, kamar yadda kuma ya gaji mulkinsa.

إِنِّي وَجَدتُّ ٱمۡرَأَةٗ تَمۡلِكُهُمۡ وَأُوتِيَتۡ مِن كُلِّ شَيۡءٖ وَلَهَا
عَرۡشٌ عَظِيمٞ ٢٣ وَجَدتُّهَا وَقَوۡمَهَا يَسۡجُدُونَ لِلشَّمۡسِ
مِن دُونِ ٱللَّهِ وَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَعۡمَٰلَهُمۡ فَصَدَّهُمۡ عَنِ ٱلسَّبِيلِ
فَهُمۡ لَا يَهۡتَدُونَ ٢٤ أَلَّا يَسۡجُدُواْ لِلَّهِ ٱلَّذِي يُخۡرِجُ ٱلۡخَبۡءَ فِي
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَيَعۡلَمُ مَا تُخۡفُونَ وَمَا تُعۡلِنُونَ ٢٥ ٱللَّهُ
لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ رَبُّ ٱلۡعَرۡشِ ٱلۡعَظِيمِ ٢٦ ۞ قَالَ سَنَنظُرُ
أَصَدَقۡتَ أَمۡ كُنتَ مِنَ ٱلۡكَٰذِبِينَ ٢٧ ٱذۡهَب بِّكِتَٰبِي هَٰذَا
فَأَلۡقِهۡ إِلَيۡهِمۡ ثُمَّ تَوَلَّ عَنۡهُمۡ فَٱنظُرۡ مَاذَا يَرۡجِعُونَ ٢٨ قَالَتۡ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلۡمَلَؤُاْ إِنِّيٓ أُلۡقِيَ إِلَيَّ كِتَٰبٞ كَرِيمٌ ٢٩ إِنَّهُۥ مِن سُلَيۡمَٰنَ وَإِنَّهُۥ
بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ٣٠ أَلَّا تَعۡلُواْ عَلَيَّ وَأۡتُونِي مُسۡلِمِينَ ٣١
قَالَتۡ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡمَلَؤُاْ أَفۡتُونِي فِيٓ أَمۡرِي مَا كُنتُ قَاطِعَةً أَمۡرًا حَتَّىٰ
تَشۡهَدُونِ ٣٢ قَالُواْ نَحۡنُ أُوْلُواْ قُوَّةٖ وَأُوْلُواْ بَأۡسٖ شَدِيدٖ وَٱلۡأَمۡرُ
إِلَيۡكِ فَٱنظُرِي مَاذَا تَأۡمُرِينَ ٣٣ قَالَتۡ إِنَّ ٱلۡمُلُوكَ إِذَا دَخَلُواْ قَرۡيَةً
أَفۡسَدُوهَا وَجَعَلُوٓاْ أَعِزَّةَ أَهۡلِهَآ أَذِلَّةٗۚ وَكَذَٰلِكَ يَفۡعَلُونَ ٣٤
وَإِنِّي مُرۡسِلَةٌ إِلَيۡهِم بِهَدِيَّةٖ فَنَاظِرَةُۢ بِمَ يَرۡجِعُ ٱلۡمُرۡسَلُونَ ٣٥

(23) “(Shi ne) lalle na sami wata mace tana mulkar su, an kuma ba ta daga kowane abu (na mulki), tana kuma da gadon sarauta mai girma
(24) “Na same ta ita da mutanenta suna sujjada ga rana ba Allah ba. Shaiɗan kuma ya ƙawata musu ayyukansu, sai ya kange su daga bin hanya ta gaskiya, don haka su ba sa kan shiriya
(25) “Don kada su yi sujjada ga Allah wanda Yake fito da abin da yake ɓoye a cikin sammai da ƙasa, kuma Yake sane da abin da kuke ɓoyewa da abin da kuke bayyanawa
(26) “(Shi ne) Allah Wanda babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, Ubangijin Al’arshi mai girma.”
(27) Sai (Sulaimana) ya ce: “To za mu duba ko ka yi gaskiya ko kuwa ka zama cikin maƙaryata
(28) “Ka tafi da wannan wasiƙar tawa sai ka jefa musu ita sannan ka ja da baya kaɗan, sai ka ga da me za su mayar da martani?”
(29) Sai ta ce: “Ya ku manyan fada, lalle an jefo min wata wasiƙa mai daraja
(30) “(Mai cewa): Lalle wannan (wasiƙar) daga Sulaimana ne kuma lalle ina farawa da Bismillahi Arrahamani Arrahim
(31) “Kada ku yi min girman kai, ku zo min kuna masu miƙa wuya!”
(32) (Sai Sarauniyar) ta ce: “Ya ku manyan fada, ku ba ni shawara game da al’amarina, (domin) ni ba zan yanke (shawarar) wani al’amari ba sai kuna nan.”
(33) Sai suka ce: “Mu dai ƙarfafa ne kuma mayaƙa sosai, al’amarin kuwa yana hannunki, sai ki duba abin da za ki yi umarni.”
(34) Sai ta ce: “Lalle sarakuna idan suka shigo wata alƙarya sai su yi kaca-kaca da ita, kuma su mayar da manyanta ƙasƙantattu; kuma haka suke aikatawa
(35) “Ni kam lalle zan aika musu ne da wata kyauta sannan in saurari abin da manzanni za su dawo da shi.”

فَلَمَّا جَآءَ سُلَيۡمَٰنَ قَالَ أَتُمِدُّونَنِ بِمَالٖ فَمَآ ءَاتَىٰنِۦَ ٱللَّهُ خَيۡرٞ مِّمَّآ
ءَاتَىٰكُم بَلۡ أَنتُم بِهَدِيَّتِكُمۡ تَفۡرَحُونَ ٣٦ ٱرۡجِعۡ إِلَيۡهِمۡ فَلَنَأۡتِيَنَّهُمۡ
بِجُنُودٖ لَّا قِبَلَ لَهُم بِهَا وَلَنُخۡرِجَنَّهُم مِّنۡهَآ أَذِلَّةٗ وَهُمۡ صَٰغِرُونَ ٣٧
قَالَ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡمَلَؤُاْ أَيُّكُمۡ يَأۡتِينِي بِعَرۡشِهَا قَبۡلَ أَن يَأۡتُونِي مُسۡلِمِينَ
٣٨ قَالَ عِفۡرِيتٞ مِّنَ ٱلۡجِنِّ أَنَا۠ ءَاتِيكَ بِهِۦ قَبۡلَ أَن تَقُومَ مِن مَّقَامِكَۖ
وَإِنِّي عَلَيۡهِ لَقَوِيٌّ أَمِينٞ ٣٩ قَالَ ٱلَّذِي عِندَهُۥ عِلۡمٞ مِّنَ ٱلۡكِتَٰبِ أَنَا۠
ءَاتِيكَ بِهِۦ قَبۡلَ أَن يَرۡتَدَّ إِلَيۡكَ طَرۡفُكَۚ فَلَمَّا رَءَاهُ مُسۡتَقِرًّا عِندَهُۥ
قَالَ هَٰذَا مِن فَضۡلِ رَبِّي لِيَبۡلُوَنِيٓ ءَأَشۡكُرُ أَمۡ أَكۡفُرُۖ وَمَن شَكَرَ فَإِنَّمَا
يَشۡكُرُ لِنَفۡسِهِۦۖ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ رَبِّي غَنِيٌّ كَرِيمٞ ٤٠ قَالَ نَكِّرُواْ لَهَا
عَرۡشَهَا نَنظُرۡ أَتَهۡتَدِيٓ أَمۡ تَكُونُ مِنَ ٱلَّذِينَ لَا يَهۡتَدُونَ ٤١ فَلَمَّا
جَآءَتۡ قِيلَ أَهَٰكَذَا عَرۡشُكِۖ قَالَتۡ كَأَنَّهُۥ هُوَۚ وَأُوتِينَا ٱلۡعِلۡمَ مِن قَبۡلِهَا
وَكُنَّا مُسۡلِمِينَ ٤٢ وَصَدَّهَا مَا كَانَت تَّعۡبُدُ مِن دُونِ ٱللَّهِۖ إِنَّهَا كَانَتۡ مِن
قَوۡمٖ كَٰفِرِينَ ٤٣ قِيلَ لَهَا ٱدۡخُلِي ٱلصَّرۡحَۖ فَلَمَّا رَأَتۡهُ حَسِبَتۡهُ لُجَّةٗ
وَكَشَفَتۡ عَن سَاقَيۡهَاۚ قَالَ إِنَّهُۥ صَرۡحٞ مُّمَرَّدٞ مِّن قَوَارِيرَۗ قَالَتۡ رَبِّ
إِنِّي ظَلَمۡتُ نَفۡسِي وَأَسۡلَمۡتُ مَعَ سُلَيۡمَٰنَ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٤٤

(36) To lokacin da (manzo) ya zo wa Sulaimanu sai ya ce: “Yanzu kwa ƙare ni da wata dukiya, alhali abin da Allah Ya ba ni ya fi wanda Ya ba ku? A’a, ku ne kuke farin ciki da kyautarku
(37) “Koma musu (da kyautarsu) sannan (ka gaya musu) lalle za mu zo musu da runduna wadda ba za su iya tunkarar ta ba, kuma lalle za mu fitar da su daga cikinta (alƙaryar) a wulaƙance suna ƙasƙantattu!”
(38) Sai (Sulaimanu) ya ce: “Ya ku manyan fada, wane ne daga cikinku zai zo min da gadon mulkinta tun kafin su zo min suna masu miƙa wuya?”
(39) Sai wani ifritu[1] daga cikin aljannu ya ce: “Ni zan zo maka da shi kafin ka tashi daga majalisarka; lalle ni kuma mai ƙarfi ne amintacce game da (kawo) shi.”
(40) Sai wani (mutum) wanda yake da ilimin Littafi (na Attaura) ya ce: “Ni zan kawo maka shi kafin ka ƙifta idonka!” To lokacin da (Sulaimanu) ya gan shi ga shi nan a gabansa sai ya ce: “Wannan yana daga falalar Ubangijina don Ya jarraba ni (Ya gani) shin zan gode ne ko zan butulce; to duk wanda ya gode kansa ya yi wa; wanda kuwa ya butulce, to lalle Ubangijina Mawadaci ne, Mai karamci.”
(41) (Sai Sulaimanu) ya ce: “Ku sauya kamannin gadon nata mu gani za ta gane (shi) ko kuwa za ta zamanto cikin waɗanda ba sa ganewa?”
(42) To lokacin da ta zo, sai aka ce (da ita): “Shin haka kuwa gadonki yake?” Sai ta ce: “Sai ka ce shi.” (Sulaimanu ya ce): “An kuwa ba mu ilimi tun gabaninta, kuma mun kasance Musulmi
(43) “Kuma abin da ta kasance tana bauta wa ba Allah ba, shi ya hana ta (yin imani); lalle ita ta kasance cikin mutane kafurai.”
(44) Aka ce da ita: “Ki shiga fadar;” to lokacin da ta gan ta sai ta zace ta ruwa ne mai zurfi, sai kuwa ta yaye ƙwaurinta. Sai (Sulaimanu) ya ce: “Ai ita fada ce da aka gina da gogaggun kasaken ƙarau (ruwa yake gudana ta ƙarƙashinsu).” Ta ce: “Ya Ubangijina, haƙiƙa na zalunci kaina, na kuma miƙa wuya ga Allah Ubangijin talikai tare da Sulaimanu.”

(1) Watau wani qaqqarfan aljani.

وَلَقَدْ أَرْسَلْنَآ إِلَىٰ ثَمُودَ أَخَاهُمْ صَٰلِحًا أَنِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ
فَإِذَا هُمْ فَرِيقَانِ يَخْتَصِمُونَ ﴿٤٥﴾ قَالَ يَٰقَوْمِ لِمَ تَسْتَعْجِلُونَ
بِٱلسَّيِّئَةِ قَبْلَ ٱلْحَسَنَةِ ۖ لَوْلَا تَسْتَغْفِرُونَ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمْ
تُرْحَمُونَ ﴿٤٦﴾ قَالُوا۟ ٱطَّيَّرْنَا بِكَ وَبِمَن مَّعَكَ ۚ قَالَ طَٰٓئِرُكُمْ
عِندَ ٱللَّهِ ۖ بَلْ أَنتُمْ قَوْمٌ تُفْتَنُونَ ﴿٤٧﴾ وَكَانَ فِى ٱلْمَدِينَةِ
تِسْعَةُ رَهْطٍ يُفْسِدُونَ فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا يُصْلِحُونَ ﴿٤٨﴾
قَالُوا۟ تَقَٰسَمُوا۟ بِٱللَّهِ لَنُبَيِّتَنَّهُۥ وَأَهْلَهُۥ ثُمَّ لَنَقُولَنَّ لِوَلِيِّهِۦ
مَا شَهِدْنَا مَهْلِكَ أَهْلِهِۦ وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَ ﴿٤٩﴾ وَمَكَرُوا۟
مَكْرًا وَمَكَرْنَا مَكْرًا وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿٥٠﴾ فَٱنظُرْ
كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ مَكْرِهِمْ أَنَّا دَمَّرْنَٰهُمْ وَقَوْمَهُمْ
أَجْمَعِينَ ﴿٥١﴾ فَتِلْكَ بُيُوتُهُمْ خَاوِيَةًۢ بِمَا ظَلَمُوٓا۟ ۗ إِنَّ
فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً لِّقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ﴿٥٢﴾ وَأَنجَيْنَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟
وَكَانُوا۟ يَتَّقُونَ ﴿٥٣﴾ وَلُوطًا إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦٓ أَتَأْتُونَ
ٱلْفَٰحِشَةَ وَأَنتُمْ تُبْصِرُونَ ﴿٥٤﴾ أَئِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ ٱلرِّجَالَ
شَهْوَةً مِّن دُونِ ٱلنِّسَآءِ ۚ بَلْ أَنتُمْ قَوْمٌ تَجْهَلُونَ ﴿٥٥﴾

(45) Hakika kuma Mun aiko wa Samudawa dan'uwansu Salihu da cewa: "Ku bauta wa Allah," sai ga su sun rabu kungiyoyi biyu[1] suna jayayya
(46) Ya ce: "Ya ku mutanena, don me kuke neman gaggautowar mummunan sakamako tun gabanin kyakkyawa[2]? Don me ba za ku nemi gafarar Allah ba don a ji kan ku."
(47) Sai suka ce: "Mu mun camfa ka kai da wadanda suke tare da kai." Sai ya ce: "Camfinku na ga Allah. A'a, ku dai mutane ne da ake jarraba ku."
(48) A cikin birnin kuma akwai wani gungu na mutum tara wadanda suke barna a bayan kasa kuma ba sa gyara
(49) Sai suka ce wa (juna): "Ku rantse da Allah cewa, lalle za mu kashe shi cikin dare shi da iyalinsa, sannan za mu fada wa mai neman jininsa cewa, ba mu halarci wurin kashe iyalinsa ba, kuma lalle mu masu gaskiya ne."
(50) Kuma suka shirya makirci, Mu kuma Muka shirya rusa makircinsu alhali kuwa su ba su sani ba
(51) Sai ka duba ka ga yadda karshen makircinsu ya zama, watau Mun hallakar da su tare da mutanensu baki daya
(52) To ga gidajensu can a rugurguje babu kowa saboda zaluncinsu. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya ga mutanen da suke ganewa
(53) Muka kuma tserar da wadanda suka yi imani, suka kuma kasance suna kiyaye dokokin Allah
(54) Kuma ka (ambaci) Ludu lokacin da ya ce da mutanensa: "Yanzu kwa rika zaike wa alfasha alhali kuwa kuna gani?
(55) "Yanzu kwa rika zaike wa maza don sha'awa ba mata ba? A'a, ku dai wasu irin mutane ne da kuke da jahilci"

(1) Watau qungiya ta farko su ne waxanda suka yi imani da Annabi Salihu, qungiya ta biyu su ne waxanda suka kafirce masa.

(2) Watau suna neman a kawo musu azaba, maimakon su roqi rahamar Allah.

فَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُوٓا۟ أَخْرِجُوٓا۟ ءَالَ
لُوطٍ مِّن قَرْيَتِكُمْ ۖ إِنَّهُمْ أُنَاسٌ يَتَطَهَّرُونَ ﴿٥٦﴾ فَأَنجَيْنَٰهُ
وَأَهْلَهُۥٓ إِلَّا ٱمْرَأَتَهُۥ قَدَّرْنَٰهَا مِنَ ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿٥٧﴾ وَأَمْطَرْنَا
عَلَيْهِم مَّطَرًا ۖ فَسَآءَ مَطَرُ ٱلْمُنذَرِينَ ﴿٥٨﴾ قُلِ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ
وَسَلَٰمٌ عَلَىٰ عِبَادِهِ ٱلَّذِينَ ٱصْطَفَىٰٓ ۗ ءَآللَّهُ خَيْرٌ أَمَّا يُشْرِكُونَ
﴿٥٩﴾ أَمَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَأَنزَلَ لَكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ
مَآءً فَأَنۢبَتْنَا بِهِۦ حَدَآئِقَ ذَاتَ بَهْجَةٍ مَّا كَانَ لَكُمْ أَن
تُنۢبِتُوا۟ شَجَرَهَآ ۗ أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِ ۚ بَلْ هُمْ قَوْمٌ يَعْدِلُونَ ﴿٦٠﴾
أَمَّن جَعَلَ ٱلْأَرْضَ قَرَارًا وَجَعَلَ خِلَٰلَهَآ أَنْهَٰرًا وَجَعَلَ
لَهَا رَوَٰسِىَ وَجَعَلَ بَيْنَ ٱلْبَحْرَيْنِ حَاجِزًا ۗ أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِ ۚ
بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٦١﴾ أَمَّن يُجِيبُ ٱلْمُضْطَرَّ إِذَا
دَعَاهُ وَيَكْشِفُ ٱلسُّوٓءَ وَيَجْعَلُكُمْ خُلَفَآءَ ٱلْأَرْضِ ۗ
أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِ ۚ قَلِيلًا مَّا تَذَكَّرُونَ ﴿٦٢﴾ أَمَّن يَهْدِيكُمْ فِى
ظُلُمَٰتِ ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ وَمَن يُرْسِلُ ٱلرِّيَٰحَ بُشْرًۢا بَيْنَ يَدَىْ
رَحْمَتِهِۦٓ ۗ أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِ ۚ تَعَٰلَى ٱللَّهُ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٦٣﴾

(56) To babu wata amsa da ta fito daga bakin mutanensa sai kawai suka ce: “Ku fitar da Luɗu shi da iyalinsa daga alƙaryarku; lalle su mutane ne da suke nuna su masu tsarki ne.”
(57) Sai Muka tserar da shi tare da iyalinsa in ban da matarsa da Muka ƙaddara ta cikin hallakakku
(58) Muka kuma yi musu ruwan azaba; to ruwan azabar waɗanda aka yi wa gargaɗi ya munana
(59) Ka ce: “Yabo ya tabbata ga Allah, kuma aminci ya tabbata ga bayinsa waɗanda Ya zaɓa.” Yanzu Allah ne Ya fi ko kuwa abin da suke tarawa (da Shi)?
(60) Ko kuwa wane ne ya halicci sammai da ƙasa, ya kuma saukar muku da ruwa daga sama, sannan Muka tsirar da (shukokin) gonaki masu ƙayatarwa, ba kuwa za ku iya tsirar da bishiyoyinsu ba? Shin akwai wani abin bauta na gaskiya tare da Allah? A’a, su dai mutane ne da suke kauce wa gaskiya
(61) Ko kuwa wane ne ya sanya ƙasa wurin zama, ya kuma sanya ƙoramu a tsattsakinta, kuma ya sanya mata turaku, kana kuma ya sanya shamaki tsakanin kogunan nan biyu (na ruwan daɗi da na ruwan zartsi)? Shin akwai wani abin bauta da gaskiya tare da Allah? A’a, yawancinsu dai ba sa ganewa
(62) Ko kuwa wane ne yake amsa wa wanda yake cikin matsuwa lokacin da ya roƙe shi, yake kuma yaye duk wani bala’i, yake kuma sanya ku halifofi a bayan ƙasa(1)? Shin akwai wani abin bauta da gaskiya tare da Allah? Kaɗan ne ƙwarai kuke wa’azantuwa
(63) Ko kuwa wane ne yake shiryar da ku a cikin duffan tudu da na kogi, kuma wane ne yake sako iska tana mai bushara gabanin (saukar) rahamarsa? Shin akwai wani abin bauta da gaskiya tare da Allah? Allah Ya ɗaukaka daga abin da suke tara (Shi da shi)

(1) Wasu su shuxe wasu su zo su gaje su, tsareku bayan tsareku.

أَمَّن يَبْدَؤُا۟ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ وَمَن يَرْزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ ۗ
أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِ ۚ قُلْ هَاتُوا۟ بُرْهَٰنَكُمْ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٦٤﴾ قُل
لَّا يَعْلَمُ مَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ٱلْغَيْبَ إِلَّا ٱللَّهُ ۚ وَمَا يَشْعُرُونَ
أَيَّانَ يُبْعَثُونَ ﴿٦٥﴾ بَلِ ٱدَّٰرَكَ عِلْمُهُمْ فِى ٱلْءَاخِرَةِ ۚ بَلْ هُمْ فِى
شَكٍّ مِّنْهَا ۖ بَلْ هُم مِّنْهَا عَمُونَ ﴿٦٦﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ أَءِذَا
كُنَّا تُرَٰبًا وَءَابَآؤُنَآ أَئِنَّا لَمُخْرَجُونَ ﴿٦٧﴾ لَقَدْ وُعِدْنَا هَٰذَا
نَحْنُ وَءَابَآؤُنَا مِن قَبْلُ إِنْ هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٦٨﴾
قُلْ سِيرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ فَٱنظُرُوا۟ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُجْرِمِينَ
﴿٦٩﴾ وَلَا تَحْزَنْ عَلَيْهِمْ وَلَا تَكُن فِى ضَيْقٍ مِّمَّا يَمْكُرُونَ ﴿٧٠﴾
وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلْوَعْدُ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٧١﴾ قُلْ عَسَىٰٓ
أَن يَكُونَ رَدِفَ لَكُم بَعْضُ ٱلَّذِى تَسْتَعْجِلُونَ ﴿٧٢﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ
لَذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَشْكُرُونَ ﴿٧٣﴾ وَإِنَّ
رَبَّكَ لَيَعْلَمُ مَا تُكِنُّ صُدُورُهُمْ وَمَا يُعْلِنُونَ ﴿٧٤﴾ وَمَا مِنْ غَآئِبَةٍ
فِى ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ إِلَّا فِى كِتَٰبٍ مُّبِينٍ ﴿٧٥﴾ إِنَّ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانَ
يَقُصُّ عَلَىٰ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ أَكْثَرَ ٱلَّذِى هُمْ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿٧٦﴾

(64) Ko kuwa wane ne yake ƙagar halitta sannan ya dawo da ita (bayan mutuwa), kuma wane ne yake arzuta ku ta sama da ƙasa? Shin akwai wani abin bauta da gaskiya tare da Allah?” Ka ce (da su): “Ku kawo dalilinku idan kun kasance masu gaskiya.”

(65) Ka ce (da su): “Duk wanda yake cikin sammai da ƙasa in ba Allah ba ba wanda ya san gaibu. Su kuma ba su san lokacin da za a tashe su ba.”

(66) A’a, iliminsu game da ranar lahira ya bibiyi na junansu[1] ne. Ba ma wannan kaɗai ba, hakanan suna cikin kokwanto ne game da ita. Ban da hakan ma, su dai makafi ne game da ita

(67) Waɗanda suka kafirta, kuma suka ce: “Yanzu bayan mun zama ƙasa mu da iyayenmu, ashe lalle za a (sake) fito da mu?

(68) “Haƙiƙa an yi mana alƙawarin wannan mu da iyayenmu tun a da can, wannan ba komai ba ne face tatsuniyoyin mutanen farko.”

(69) Ka ce (da su): “Ku yi tafiya a bayan ƙasa za ku ga yadda ƙarshen kafurai ya kasance.”

(70) Kuma kada ranka ya ɓaci game da su, kada kuma ka zama cikin ƙuncin zuciya game da makircin da suke ƙullawa

(71) Suna kuma cewa: “Yaushe ne lokacin wannan wa’adin idan kun kasance masu gaskiya?”

(72) Ka ce (da su): “Lalle sashin abin da kuke gaggauto da zuwansa (na azaba) ya kusanto.”

(73) Kuma lalle Ubangijinka Mai falala ne ga mutane, sai dai kuma yawancinsu ba sa godewa

(74) Lalle kuma Ubangijinka tabbas Yana sane da abin da zukatansu suke ɓoyewa, da kuma abin da suke bayyanawa

(75) Kuma babu wani abu da yake ɓoye a cikin sammai da ƙasa face yana cikin littafi mabayyani (watau Lauhul-Mahafuzu)

(76) Lalle wannan Alƙur’anin yana labarta wa Banu-Isra’ila mafi yawan abin da suke saɓani a kansa

(1) Watau sun sami iliminsu game da lahira daga iyayensu, su ma daga nasu iyayen, watau abin da ya shahara a wajensuna qaryata ranar alqiyama.

وَإِنَّهُۥ لَهُدًى وَرَحْمَةٌ لِّلْمُؤْمِنِينَ ﴿٧٧﴾ إِنَّ رَبَّكَ يَقْضِى بَيْنَهُم
بِحُكْمِهِۦ ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٧٨﴾ فَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِ ۖ إِنَّكَ عَلَى
ٱلْحَقِّ ٱلْمُبِينِ ﴿٧٩﴾ إِنَّكَ لَا تُسْمِعُ ٱلْمَوْتَىٰ وَلَا تُسْمِعُ ٱلصُّمَّ ٱلدُّعَآءَ
إِذَا وَلَّوْا۟ مُدْبِرِينَ ﴿٨٠﴾ وَمَآ أَنتَ بِهَٰدِى ٱلْعُمْىِ عَن ضَلَٰلَتِهِمْ ۖ إِن
تُسْمِعُ إِلَّا مَن يُؤْمِنُ بِـَٔايَٰتِنَا فَهُم مُّسْلِمُونَ ﴿٨١﴾ ۞ وَإِذَا وَقَعَ
ٱلْقَوْلُ عَلَيْهِمْ أَخْرَجْنَا لَهُمْ دَآبَّةً مِّنَ ٱلْأَرْضِ تُكَلِّمُهُمْ أَنَّ
ٱلنَّاسَ كَانُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا لَا يُوقِنُونَ ﴿٨٢﴾ وَيَوْمَ نَحْشُرُ مِن كُلِّ أُمَّةٍ
فَوْجًا مِّمَّن يُكَذِّبُ بِـَٔايَٰتِنَا فَهُمْ يُوزَعُونَ ﴿٨٣﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُو قَالَ
أَكَذَّبْتُم بِـَٔايَٰتِى وَلَمْ تُحِيطُوا۟ بِهَا عِلْمًا أَمَّاذَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ
﴿٨٤﴾ وَوَقَعَ ٱلْقَوْلُ عَلَيْهِم بِمَا ظَلَمُوا۟ فَهُمْ لَا يَنطِقُونَ ﴿٨٥﴾ أَلَمْ
يَرَوْا۟ أَنَّا جَعَلْنَا ٱلَّيْلَ لِيَسْكُنُوا۟ فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبْصِرًا ۚ إِنَّ فِى
ذَٰلِكَ لَـَٔايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٨٦﴾ وَيَوْمَ يُنفَخُ فِى ٱلصُّورِ فَفَزِعَ مَن
فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِى ٱلْأَرْضِ إِلَّا مَن شَآءَ ٱللَّهُ ۚ وَكُلٌّ أَتَوْهُ
دَٰخِرِينَ ﴿٨٧﴾ وَتَرَى ٱلْجِبَالَ تَحْسَبُهَا جَامِدَةً وَهِىَ تَمُرُّ مَرَّ ٱلسَّحَابِ ۚ
صُنْعَ ٱللَّهِ ٱلَّذِىٓ أَتْقَنَ كُلَّ شَىْءٍ ۚ إِنَّهُۥ خَبِيرٌۢ بِمَا تَفْعَلُونَ ﴿٨٨﴾

(77) Lalle kuma shi (Alkur'ani) tabbas shiriya ne kuma rahama ce ga muminai
(78) Lalle Ubangijinka zai yi shari'a a tsakaninsu da hukuncinsa. Shi kuwa Mabuwayi ne, Masani
(79) To ka dogara ga Allah; lalle kai kana kan gaskiya mabayyaniya
(80) Lalle kai ba ka iya jiyar da matattu, ba kuma ka iya jiyar da kurame kira lokacin da suka juya suna masu ba da baya
(81) Kuma sannan kai ba za ka iya shiryar da makafi daga ɓatansu ba; ba wanda kake iya jiyarwa sai wanda ya yi imani da ayoyinmu, to waɗannan su ne Musulmi
(82) Kuma idan lokacin da aka alkawarta musu ya cika, to za Mu fito musu da wata dabba daga ƙasa[1] da za ta rika faɗa musu cewa: "Lalle mutane sun zamanto ba sa sakankancewa da ayoyinmu."
(83) Kuma ka tuna ranar da za Mu tattara jama'a na kowacce al'umma, daga cikin waɗanda suke ƙaryata ayoyinmu ana koro su na farko da na ƙarshe
(84) Har yayin da suka zo (sannan Allah) Ya ce da su: "Yanzu ku kuka ƙaryata ayoyina, alhali kuwa ba ku tantance da saninsu ba? Ko kuwa me kuka zamanto kuna aikatawa ne (a duniya)?"
(85) Kuma abin da aka alkawarta musu na azaba ya tabbata a kansu saboda kafircinsu, to su ba za su iya furta komai ba
(86) Yanzu ba sa gani cewa Mu Muka samar da dare don su nutsu a cikinsa, da kuma rana mai haskakawa (don su yi harka)? Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutanen da suke yin imani
(87) (Ka tuna) kuma ranar da za a busa ƙaho sai duk mahalukin da yake cikin sammai da ƙasa ya firgita, sai dai wanda Allah Ya toge. Kuma gaba ɗayansu za su zo masa suna masu mika wuya
(88) Kuma za ka ga duwatsu ka zaci a tsaye suke cak, alhali kuwa su suna tafiya ne irin tafiyar gizagizai. Aikin Allah kenan wanda Ya kyautata halittar kowane irin abu. Lalle Shi Masanin abin da kuke aikatawa ne

(1) Wannan xaya ce daga cikin manyan alamomin alqiyama, watau fitowar wata dabba mai magana da mutane.

مَن جَآءَ بِٱلۡحَسَنَةِ فَلَهُۥ خَيۡرٞ مِّنۡهَا وَهُم مِّن فَزَعٖ يَوۡمَئِذٍ ءَامِنُونَ ٨٩
وَمَن جَآءَ بِٱلسَّيِّئَةِ فَكُبَّتۡ وُجُوهُهُمۡ فِي ٱلنَّارِ هَلۡ تُجۡزَوۡنَ إِلَّا
مَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٩٠ إِنَّمَآ أُمِرۡتُ أَنۡ أَعۡبُدَ رَبَّ هَٰذِهِ ٱلۡبَلۡدَةِ
ٱلَّذِي حَرَّمَهَا وَلَهُۥ كُلُّ شَيۡءٖۖ وَأُمِرۡتُ أَنۡ أَكُونَ مِنَ ٱلۡمُسۡلِمِينَ
٩١ وَأَنۡ أَتۡلُوَاْ ٱلۡقُرۡءَانَۖ فَمَنِ ٱهۡتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهۡتَدِي لِنَفۡسِهِۦۖ
وَمَن ضَلَّ فَقُلۡ إِنَّمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلۡمُنذِرِينَ ٩٢ وَقُلِ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ
سَيُرِيكُمۡ ءَايَٰتِهِۦ فَتَعۡرِفُونَهَاۚ وَمَا رَبُّكَ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ٩٣

سُورَةُ القَصَصِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

طسٓمٓ ١ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡمُبِينِ ٢ نَتۡلُواْ عَلَيۡكَ
مِن نَّبَإِ مُوسَىٰ وَفِرۡعَوۡنَ بِٱلۡحَقِّ لِقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٣ إِنَّ
فِرۡعَوۡنَ عَلَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَجَعَلَ أَهۡلَهَا شِيَعٗا يَسۡتَضۡعِفُ
طَآئِفَةٗ مِّنۡهُمۡ يُذَبِّحُ أَبۡنَآءَهُمۡ وَيَسۡتَحۡيِۦ نِسَآءَهُمۡۚ إِنَّهُۥ كَانَ
مِنَ ٱلۡمُفۡسِدِينَ ٤ وَنُرِيدُ أَن نَّمُنَّ عَلَى ٱلَّذِينَ ٱسۡتُضۡعِفُواْ
فِي ٱلۡأَرۡضِ وَنَجۡعَلَهُمۡ أَئِمَّةٗ وَنَجۡعَلَهُمُ ٱلۡوَٰرِثِينَ ٥

(89) Duk wadanda suka zo da kyakkyawan (aiki), to suna da (lada) fiye da shi, kuma su amintattu ne daga firgitar wannan ranar
(90) Wadanda kuwa suka zo da mummunan (aiki), to an kifar da fuskokinsu cikin wuta, to ba za a saka muku ba sai da irin abin da kuka zamanto kuna aikatawa
(91) (Ka ce da su): “Ni dai an umarce ni ne kawai da in bauta wa Ubangijin wannan garin (Makka) wanda Ya mayar da shi mai alfarma, kuma komai nasa ne; kuma an umarce ni da in zama cikin Musulmi
(92) “An kuma (umarce ni) da in karanta Alkur’ani; don haka duk wanda ya shiriya, to ya shiriya ne don amfanin kansa; wanda kuwa ya bace sai ka ce (da shi): ‘Da ma ni ina cikin masu gargadi ne kawai’”
(93) Ka kuma ce: “Dukkan yabo ya tabbata ga Allah; ba da dadewa ba zai nuna muku ayoyinsa, za kuma ku san su. Ubangijinka kuma ba rafkananne ba ne game da abin da kuke aikatawa.”myatendayo

Sura Kasas

(1) DA SIN MIM[1]
(2) Wadannan ayoyi ne na Littafi mabayyani
(3) Muna karanta maka labarin Musa da Fir’auna da gaskiya don mutane da suke yin imani
(4) Lalle Fir’auna ya yi dagawa a cikin kasar (Masar) ya kuma mayar da mutanenta kungiyoyi daban-daban, yana bautar da wata kungiyar daga cikinsu, yana yanka ‘ya’yayensu maza, yana kuma kyale matansu da rai. Lalle shi ya kasance cikin mabarnata
(5) Muna kuma nufin za Mu yi baiwa ga wadanda aka wulakanta a cikin kasar (Masar) Mu kuma mayar da su shugabanni, kuma Mu mayar da su magadan (mulkin Fir’auna)

(1) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8.

وَنُمَكِّنَ لَهُمْ فِي ٱلْأَرْضِ وَنُرِيَ فِرْعَوْنَ وَهَٰمَٰنَ وَجُنُودَهُمَا
مِنْهُم مَّا كَانُوا۟ يَحْذَرُونَ ﴿٦﴾ وَأَوْحَيْنَآ إِلَىٰٓ أُمِّ مُوسَىٰٓ
أَنْ أَرْضِعِيهِ ۖ فَإِذَا خِفْتِ عَلَيْهِ فَأَلْقِيهِ فِي ٱلْيَمِّ وَلَا تَخَافِي
وَلَا تَحْزَنِىٓ ۖ إِنَّا رَآدُّوهُ إِلَيْكِ وَجَاعِلُوهُ مِنَ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿٧﴾
فَٱلْتَقَطَهُۥٓ ءَالُ فِرْعَوْنَ لِيَكُونَ لَهُمْ عَدُوًّا وَحَزَنًا ۗ إِنَّ
فِرْعَوْنَ وَهَٰمَٰنَ وَجُنُودَهُمَا كَانُوا۟ خَٰطِـِٔينَ ﴿٨﴾
وَقَالَتِ ٱمْرَأَتُ فِرْعَوْنَ قُرَّتُ عَيْنٍ لِّى وَلَكَ ۖ لَا تَقْتُلُوهُ
عَسَىٰٓ أَن يَنفَعَنَآ أَوْ نَتَّخِذَهُۥ وَلَدًا وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿٩﴾
وَأَصْبَحَ فُؤَادُ أُمِّ مُوسَىٰ فَٰرِغًا ۖ إِن كَادَتْ لَتُبْدِى بِهِۦ لَوْلَآ
أَن رَّبَطْنَا عَلَىٰ قَلْبِهَا لِتَكُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١٠﴾ وَقَالَتْ
لِأُخْتِهِۦ قُصِّيهِ ۖ فَبَصُرَتْ بِهِۦ عَن جُنُبٍ وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ
﴿١١﴾ ۞ وَحَرَّمْنَا عَلَيْهِ ٱلْمَرَاضِعَ مِن قَبْلُ فَقَالَتْ هَلْ أَدُلُّكُمْ
عَلَىٰٓ أَهْلِ بَيْتٍ يَكْفُلُونَهُۥ لَكُمْ وَهُمْ لَهُۥ نَٰصِحُونَ
﴿١٢﴾ فَرَدَدْنَٰهُ إِلَىٰٓ أُمِّهِۦ كَىْ تَقَرَّ عَيْنُهَا وَلَا تَحْزَنَ وَلِتَعْلَمَ
أَنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٣﴾

(6) Mu kuma kafa su a ƙasar, kuma Mu nuna wa Fir'auna da Hamana da rundunoninsu gaba ɗayansu abin da suke jin tsoro game da su (Banu Isra'ila)
(7) Muka kuma yi wa mahaifiyar Musa wahayi da cewa: "Ki shayar da shi; to yayin da kika ji masa tsoro, sai ki jefa shi a cikin kogi, kada kuma ki ji tsoro, kuma kada ki yi baƙin ciki; lalle Mu Masu dawo miki da shi ne, kuma Masu sanya shi ne cikin manzanni."
(8) Sai mutanen Fir'auna suka tsince shi domin (daga baya) ya zama abokin gaba da kuma baƙin ciki a gare su. Lalle Fir'auna da Hamana da rundunoninsu sun kasance masu laifi
(9) Matar Fir'auna kuma ta ce: "(Shi) farin ciki ne a gare ni har da kai; kada ku kashe shi, muna fatan ya amfane mu ko kuma mu ɗauke shi a matsayin ɗa," alhali kuwa su ba su san (abin da zai faru ba)
(10) Zuciyar mahaifiyar Musa kuma ta wayi gari ba komai a cikinta (sai tunaninsa); ba shakka sauran ƙiris ta bayyana shi, ba don Mun ɗaure zuciyarta ba don ta zama cikin muminai
(11) Ta kuma ce da 'yar'uwarsa: "Ki bi sawunsa"; sai ta hango shi daga nesa, su kuwa ba su gane ita ('yar'uwarsa ba ce)
(12) Da ma kuma can Mun haramta masa (nonon) masu shayarwa(1), sai ('yar'uwar tasa) ta ce: "Yanzu ba na nuna muku mutanen wani gida da za su shayar muku da shi ba, su kuma za su kyautata masa?"
(13) Sai Muka dawo da shi wurin mahaifiyarsa don hankalinta ya kwanta kuma don kada ta yi baƙin ciki, don kuma ta san cewa alƙawarin Allah gaskiya ne, sai dai kuma yawancinsu ba sa fahimtar (haka)

(1) Watau ya qi karvar nonon duk wata mai shayarwa da aka kawo don shayar da shi a gidan Fir'auna.

وَلَمَّا بَلَغَ أَشُدَّهُۥ وَٱسْتَوَىٰٓ ءَاتَيْنَٰهُ حُكْمًا وَعِلْمًا ۚ وَكَذَٰلِكَ نَجْزِى
ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿١٤﴾ وَدَخَلَ ٱلْمَدِينَةَ عَلَىٰ حِينِ غَفْلَةٍ مِّنْ أَهْلِهَا
فَوَجَدَ فِيهَا رَجُلَيْنِ يَقْتَتِلَانِ هَٰذَا مِن شِيعَتِهِۦ وَهَٰذَا مِنْ عَدُوِّهِۦ ۖ
فَٱسْتَغَٰثَهُ ٱلَّذِى مِن شِيعَتِهِۦ عَلَى ٱلَّذِى مِنْ عَدُوِّهِۦ فَوَكَزَهُۥ
مُوسَىٰ فَقَضَىٰ عَلَيْهِ ۖ قَالَ هَٰذَا مِنْ عَمَلِ ٱلشَّيْطَٰنِ ۖ إِنَّهُۥ عَدُوٌّ مُّضِلٌّ
مُّبِينٌ ﴿١٥﴾ قَالَ رَبِّ إِنِّى ظَلَمْتُ نَفْسِى فَٱغْفِرْ لِى فَغَفَرَ لَهُۥٓ ۚ إِنَّهُۥ
هُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٦﴾ قَالَ رَبِّ بِمَآ أَنْعَمْتَ عَلَىَّ فَلَنْ أَكُونَ
ظَهِيرًا لِّلْمُجْرِمِينَ ﴿١٧﴾ فَأَصْبَحَ فِى ٱلْمَدِينَةِ خَآئِفًا يَتَرَقَّبُ فَإِذَا
ٱلَّذِى ٱسْتَنصَرَهُۥ بِٱلْأَمْسِ يَسْتَصْرِخُهُۥ ۚ قَالَ لَهُۥ مُوسَىٰٓ إِنَّكَ لَغَوِىٌّ
مُّبِينٌ ﴿١٨﴾ فَلَمَّآ أَنْ أَرَادَ أَن يَبْطِشَ بِٱلَّذِى هُوَ عَدُوٌّ لَّهُمَا قَالَ
يَٰمُوسَىٰٓ أَتُرِيدُ أَن تَقْتُلَنِى كَمَا قَتَلْتَ نَفْسًۢا بِٱلْأَمْسِ ۖ إِن تُرِيدُ
إِلَّآ أَن تَكُونَ جَبَّارًا فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا تُرِيدُ أَن تَكُونَ مِنَ ٱلْمُصْلِحِينَ
﴿١٩﴾ وَجَآءَ رَجُلٌ مِّنْ أَقْصَا ٱلْمَدِينَةِ يَسْعَىٰ قَالَ يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّ ٱلْمَلَأَ
يَأْتَمِرُونَ بِكَ لِيَقْتُلُوكَ فَٱخْرُجْ إِنِّى لَكَ مِنَ ٱلنَّٰصِحِينَ ﴿٢٠﴾
فَخَرَجَ مِنْهَا خَآئِفًا يَتَرَقَّبُ ۖ قَالَ رَبِّ نَجِّنِى مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٢١﴾

(14) Lokacin kuma da ya kai ganiyar ƙarfinsa ya kuma kammala, sai Muka ba shi hukunci da ilimi. Kamar haka kuwa Muke saka wa masu kyautatawa

(15) Sai ya shiga cikin birnin a lokacin hutawar mutanensa, sai ya sami mutum biyu a cikinsa suna faɗa; wannan ɗan ƙabilarsa ne, wannan kuma daga maƙiyansa, sai ɗan ƙabilar tasa ya nemi taimakonsa a kan wanda yake daga maƙiyansa; to sai Musa ya naushe shi, sai kuwa ya kashe shi; (da ya ga haka sai) ya ce: "Wannan yana daga aikin Shaiɗan, lalle shi kuwa maƙiyi ne mai ɓatarwa na fili."

(16) Ya ce: "Ya Ubangijina, lalle ni na zalunci kaina, sai Ka yi min gafara," sai ko Ya yi masa gafara. Lalle Shi kuwa Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(17) Ya ce: "Ya Ubangijina, saboda ni'imar da Ka yi min, ba zan taɓa zama mai taimakon masu laifi ba."

(18) Sai ya wayi gari a cikin birnin a tsorace yana ɗar-ɗar, sai ga wanda ya nemi taimakon nan nasa a jiya yana sake neman taimakonsa, (sai) Musa ya ce da shi: "Lalle kai dai ɓatacce ne a fili!"

(19) To lokacin da ya nufi wawurar abokin gabar tasu (sai mai neman taimakon) ya ce: "Ya Musa, shin yanzu nufi kake ka kashe ni kamar yadda ka kashe rai a jiya? Ba abin da kake nufi sai ka zama mai tsaurin rai a bayan ƙasa; ba ka kuma nufin ka zama cikin masu kawo gyara."

(20) Sai wani mutum (mumini daga mutanen Fir'auna) ya zo daga can ƙarshen birnin yana gaggawa, ya ce: "Ya Musa, lalle manyan gari (suna can) suna shawara a kanka don su kashe ka, to ka fita (daga birnin nan), lalle ni ina cikin masu yi maka nasiha."

(21) Sai ya fita daga cikinsa (wato birnin) a tsorace yana ta ɗar-ɗar, ya ce: "Ya Ubangijina, Ka tserar da ni daga azzaluman mutanen nan."

وَلَمَّا تَوَجَّهَ تِلْقَآءَ مَدْيَنَ قَالَ عَسَىٰ رَبِّيٓ أَن يَهْدِيَنِي سَوَآءَ
ٱلسَّبِيلِ ﴿٢٢﴾ وَلَمَّا وَرَدَ مَآءَ مَدْيَنَ وَجَدَ عَلَيْهِ أُمَّةً مِّنَ
ٱلنَّاسِ يَسْقُونَ وَوَجَدَ مِن دُونِهِمُ ٱمْرَأَتَيْنِ تَذُودَانِ ۖ قَالَ
مَا خَطْبُكُمَا ۖ قَالَتَا لَا نَسْقِي حَتَّىٰ يُصْدِرَ ٱلرِّعَآءُ ۖ وَأَبُونَا
شَيْخٌ كَبِيرٌ ﴿٢٣﴾ فَسَقَىٰ لَهُمَا ثُمَّ تَوَلَّىٰٓ إِلَى ٱلظِّلِّ فَقَالَ
رَبِّ إِنِّي لِمَآ أَنزَلْتَ إِلَيَّ مِنْ خَيْرٍ فَقِيرٌ ﴿٢٤﴾ فَجَآءَتْهُ إِحْدَىٰهُمَا
تَمْشِي عَلَى ٱسْتِحْيَآءٍ قَالَتْ إِنَّ أَبِي يَدْعُوكَ لِيَجْزِيَكَ
أَجْرَ مَا سَقَيْتَ لَنَا ۚ فَلَمَّا جَآءَهُۥ وَقَصَّ عَلَيْهِ ٱلْقَصَصَ قَالَ
لَا تَخَفْ ۖ نَجَوْتَ مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٢٥﴾ قَالَتْ إِحْدَىٰهُمَا
يَٰٓأَبَتِ ٱسْتَـْٔجِرْهُ ۖ إِنَّ خَيْرَ مَنِ ٱسْتَـْٔجَرْتَ ٱلْقَوِيُّ ٱلْأَمِينُ
﴿٢٦﴾ قَالَ إِنِّيٓ أُرِيدُ أَنْ أُنكِحَكَ إِحْدَى ٱبْنَتَيَّ هَٰتَيْنِ عَلَىٰٓ أَن
تَأْجُرَنِي ثَمَٰنِيَ حِجَجٍ ۖ فَإِنْ أَتْمَمْتَ عَشْرًا فَمِنْ عِندِكَ ۖ
وَمَآ أُرِيدُ أَنْ أَشُقَّ عَلَيْكَ ۚ سَتَجِدُنِيٓ إِن شَآءَ ٱللَّهُ مِنَ
ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿٢٧﴾ قَالَ ذَٰلِكَ بَيْنِي وَبَيْنَكَ ۖ أَيَّمَا ٱلْأَجَلَيْنِ
قَضَيْتُ فَلَا عُدْوَٰنَ عَلَيَّ ۖ وَٱللَّهُ عَلَىٰ مَا نَقُولُ وَكِيلٌ ﴿٢٨﴾

(22) Yayin da kuma ya sa gaba ya nufi wajen (birnin) Madyana, sai ya ce: “Ina fatan Ubangijina Ya shiryar da ni hanyar da ta fi dacewa.”

(23) Lokacin da kuma ya iso mashayar ruwa ta Madyana sai ya sami wani gungun mutane suna shayar (da dabbobinsu), ya kuma sami wasu mata su biyu a gefensu suna kare (dabbobinsu); sai ya ce (da su): “Me ya same ku ne?” Sai suka ce: “Mu ai ba ma shayarwa har sai duk makiyaya sun watse, kuma mahaifinmu tsoho ne tukub.”

(24) To sai ya shayar musu (da dabbobin nasu), sannan ya koma wurin wata inuwa ya ce: “Ya Ubangijina, lalle ni mabuƙacin duk wani alhairi ne da za ka hore mini!”


(25) Sai ɗayarsu ta zo masa tana tafiya cikin jin kunya ta ce: “Babana yana kiran ka don ya saka maka ladan shayarwar da ka yi mana.” To lokacin da ya zo wurinsa ya kuma ba shi labarin(sa) sai ya ce da shi: “Kada ka ji tsoro, ka tsira daga azzaluman mutane.”

(26) Sai ɗayarsu ta ce: “Babana, ka ɗauke shi aiki mana; don kuwa lalle ba wanda ya fi dacewa ka ɗauka aiki sai ƙaƙƙarfa, amintacce.”

(27) Sai ya ce da (Musa): “Ina so in aura maka ɗaya daga ‘ya’yayen nan nawa guda biyu, a kan ka yi min aiki na shekara takwas; to amma idan ka cika goma to wannan raɗin kanka ne; ba na kuwa nufin in ƙuntata maka. Za ka same ni kuwa in Allah Ya yarda daga cikin nagartattun mutane.”

(28) (Musa) ya ce: “Wannan tsakanina da kai ne; kowanne ɗayan lokatan biyu na cika to kada a ƙware ni; Allah kuwa shaida ne game da abin da muke faɗa.”

Loren ipsu


* فَلَمَّا قَضَىٰ مُوسَى ٱلْأَجَلَ وَسَارَ بِأَهْلِهِۦٓ ءَانَسَ مِن جَانِبِ
ٱلطُّورِ نَارًا قَالَ لِأَهْلِهِ ٱمْكُثُوٓا۟ إِنِّىٓ ءَانَسْتُ نَارًا لَّعَلِّىٓ ءَاتِيكُم
مِّنْهَا بِخَبَرٍ أَوْ جَذْوَةٍ مِّنَ ٱلنَّارِ لَعَلَّكُمْ تَصْطَلُونَ
٢٩ فَلَمَّآ أَتَىٰهَا نُودِىَ مِن شَـٰطِئِ ٱلْوَادِ ٱلْأَيْمَنِ فِى ٱلْبُقْعَةِ
ٱلْمُبَـٰرَكَةِ مِنَ ٱلشَّجَرَةِ أَن يَـٰمُوسَىٰٓ إِنِّىٓ أَنَا ٱللَّهُ رَبُّ
ٱلْعَـٰلَمِينَ ٣٠ وَأَنْ أَلْقِ عَصَاكَ ۖ فَلَمَّا رَءَاهَا تَهْتَزُّ كَأَنَّهَا
جَآنٌّ وَلَّىٰ مُدْبِرًا وَلَمْ يُعَقِّبْ ۚ يَـٰمُوسَىٰٓ أَقْبِلْ وَلَا تَخَفْ ۖ
إِنَّكَ مِنَ ٱلْـَٔامِنِينَ ٣١ ٱسْلُكْ يَدَكَ فِى جَيْبِكَ تَخْرُجْ
بَيْضَآءَ مِنْ غَيْرِ سُوٓءٍ وَٱضْمُمْ إِلَيْكَ جَنَاحَكَ مِنَ ٱلرَّهْبِ ۖ
فَذَانِكَ بُرْهَـٰنَانِ مِن رَّبِّكَ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِۦٓ ۚ إِنَّهُمْ
كَانُوا۟ قَوْمًا فَـٰسِقِينَ ٣٢ قَالَ رَبِّ إِنِّى قَتَلْتُ مِنْهُمْ نَفْسًا
فَأَخَافُ أَن يَقْتُلُونِ ٣٣ وَأَخِى هَـٰرُونُ هُوَ أَفْصَحُ مِنِّى لِسَانًا
فَأَرْسِلْهُ مَعِىَ رِدْءًا يُصَدِّقُنِىٓ ۖ إِنِّىٓ أَخَافُ أَن يُكَذِّبُونِ ٣٤
قَالَ سَنَشُدُّ عَضُدَكَ بِأَخِيكَ وَنَجْعَلُ لَكُمَا سُلْطَـٰنًا فَلَا
يَصِلُونَ إِلَيْكُمَا ۚ بِـَٔايَـٰتِنَآ ۚ أَنتُمَا وَمَنِ ٱتَّبَعَكُمَا ٱلْغَـٰلِبُونَ ٣٥

(29) To yayin da Musa ya cika lokacinsa ya kuma tafi da iyalinsa, sai ya hango wuta daga gefen (dutsen) Duri, ya ce: “Lalle na hango wuta, (zan je don) in zo muku da labari daga wurinta ko kuma (in samo muku) wani garwashi na wutar don ku ji ɗumi.”

(30) To lokacin da ya zo wurinta sai aka yi kira daga gefen kwari na damarsa a wani wuri mai albarka na bishiya, cewa: “Ya Musa, lalle Ni ne Allah Ubangijin talikai!

(31) “Kuma ka jefar da sandarka;” to lokacin da ya gan ta tana girgiza kamar maciji sai ya ba da baya a guje, bai ko waiwaya ba. (Aka ce da shi): “Ya Musa dawo, kada ka ji tsoro; lalle kai kana cikin amintattu

(32) “Ka sanya hannunka a cikin wuyan rigarka, zai fito fari fat ba tare da wata cuta ba, kuma ka haɗe hannunka da kwibinka saboda tsoron (farinta); to biyu ɗin nan hujjoji ne daga Ubangijinka zuwa ga Fir’auna da mutanensa. Lalle su sun kasance mutane ne fasiƙai.”

(33) (Musa) ya ce: “Ya Ubangijina, lalle ni na kashe musu wani mutum, to ina tsoron su kashe ni

(34) “Kuma ɗan’uwana Haruna shi ya fi ni fasahar harshe, sai Ka aike shi tare da ni ya zama mataimakina yana gaskata ni; lalle ni ina jin tsoron su ƙaryata ni.”

(35) (Sai Allah) Ya ce: “Za Mu ƙarfafa dantsenka da ɗan’uwanka kuma za Mu sanya muku wata hujja, don haka ba za su isa gare ku (da cuta) ba. Da ayoyinmu - ku da waɗanda suka bi ku - ku ne masu yin galaba.”

فَلَمَّا جَآءَهُم مُّوسَىٰ بِـَٔايَـٰتِنَا بَيِّنَـٰتٍ قَالُوا۟ مَا هَـٰذَآ إِلَّا سِحْرٌ
مُّفْتَرًى وَمَا سَمِعْنَا بِهَـٰذَا فِىٓ ءَابَآئِنَا ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٣٦﴾
وَقَالَ مُوسَىٰ رَبِّىٓ أَعْلَمُ بِمَن جَآءَ بِٱلْهُدَىٰ مِنْ عِندِهِۦ وَمَن
تَكُونُ لَهُۥ عَـٰقِبَةُ ٱلدَّارِ ۖ إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ ٱلظَّـٰلِمُونَ ﴿٣٧﴾
وَقَالَ فِرْعَوْنُ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلْمَلَأُ مَا عَلِمْتُ لَكُم مِّنْ إِلَـٰهٍ
غَيْرِى فَأَوْقِدْ لِى يَـٰهَـٰمَـٰنُ عَلَى ٱلطِّينِ فَٱجْعَل لِّى صَرْحًا لَّعَلِّىٓ
أَطَّلِعُ إِلَىٰٓ إِلَـٰهِ مُوسَىٰ وَإِنِّى لَأَظُنُّهُۥ مِنَ ٱلْكَـٰذِبِينَ ﴿٣٨﴾
وَٱسْتَكْبَرَ هُوَ وَجُنُودُهُۥ فِى ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ وَظَنُّوٓا۟
أَنَّهُمْ إِلَيْنَا لَا يُرْجَعُونَ ﴿٣٩﴾ فَأَخَذْنَـٰهُ وَجُنُودَهُۥ فَنَبَذْنَـٰهُمْ
فِى ٱلْيَمِّ ۖ فَٱنظُرْ كَيْفَ كَانَ عَـٰقِبَةُ ٱلظَّـٰلِمِينَ ﴿٤٠﴾
وَجَعَلْنَـٰهُمْ أَئِمَّةً يَدْعُونَ إِلَى ٱلنَّارِ ۖ وَيَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ
لَا يُنصَرُونَ ﴿٤١﴾ وَأَتْبَعْنَـٰهُمْ فِى هَـٰذِهِ ٱلدُّنْيَا لَعْنَةً ۖ
وَيَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ هُم مِّنَ ٱلْمَقْبُوحِينَ ﴿٤٢﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا
مُوسَى ٱلْكِتَـٰبَ مِنۢ بَعْدِ مَآ أَهْلَكْنَا ٱلْقُرُونَ ٱلْأُولَىٰ
بَصَآئِرَ لِلنَّاسِ وَهُدًى وَرَحْمَةً لَّعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿٤٣﴾

(36) To lokacin da Musa ya zo musu da ayoyinmu mabayyana sai suka ce: “Ai wannan ba wani abu ba ne face ƙagaggen sihiri, mu kuma ba mu taɓa jin wannan ba a wurin iyayenmu na farko.”
(37) Musa kuma ya ce: “Ubangijina (Shi ne) Ya fi sanin wanda ya zo da shiriya daga wurinsa, da kuma wanda kyakkyawan ƙarshe zai kasance a gare shi; lalle yadda al’amarin yake, azzalumai ba sa rabauta.”
(38) Fir’auna kuma ya ce: “Ya ku manyan gari, ban san kuna da wani abin bauta ba in ba ni ba, kai ko Hamana, shirya min ƙonannen taɓo sannan ka yi min dogon gini don in hango abin bautar Musa, lalle ni ina tsammanin cewa shi yana cikin maƙaryata.”
(39) Ya kuma yi girman kai shi da rundunoninsa a ƙasar (Masar) ba da gaskiya ba, suka kuma yi tsammanin cewa su ba za a komar da su zuwa gare Mu ba
(40) Sai Muka kama shi da rundunoninsa, sannan Muka watsa su a cikin kogi; to ka duba ka ga yadda ƙarshen azzalumai ya kasance
(41) Muka kuma mayar da su shugabanni masu kira zuwa ga wuta; ranar alƙiyama kuma ba za a taimake su ba
(42) Muka kuma bi su da la’anta a wannan duniyar; ranar alƙiyama kuma suna cikin waɗanda za a jefa cikin mummunan hali
(43) Haƙiƙa kuma Mun bai wa Musa littafin (Attaura) bayan Mun hallaka al’ummu na farko don izina ga mutane da shiriya da rahama ko sa wa’azantu

وَمَا كُنتَ بِجَانِبِ ٱلْغَرْبِيِّ إِذْ قَضَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَى ٱلْأَمْرَ وَمَا كُنتَ
مِنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ﴿٤٤﴾ وَلَٰكِنَّآ أَنشَأْنَا قُرُونًا فَتَطَاوَلَ عَلَيْهِمُ
ٱلْعُمُرُ ۚ وَمَا كُنتَ ثَاوِيًا فِىٓ أَهْلِ مَدْيَنَ تَتْلُوا۟ عَلَيْهِمْ
ءَايَٰتِنَا وَلَٰكِنَّا كُنَّا مُرْسِلِينَ ﴿٤٥﴾ وَمَا كُنتَ بِجَانِبِ
ٱلطُّورِ إِذْ نَادَيْنَا وَلَٰكِن رَّحْمَةً مِّن رَّبِّكَ لِتُنذِرَ قَوْمًا
مَّآ أَتَىٰهُم مِّن نَّذِيرٍ مِّن قَبْلِكَ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿٤٦﴾
وَلَوْلَآ أَن تُصِيبَهُم مُّصِيبَةٌۢ بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ فَيَقُولُوا۟
رَبَّنَا لَوْلَآ أَرْسَلْتَ إِلَيْنَا رَسُولًا فَنَتَّبِعَ ءَايَٰتِكَ وَنَكُونَ
مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٤٧﴾ فَلَمَّا جَآءَهُمُ ٱلْحَقُّ مِنْ عِندِنَا قَالُوا۟
لَوْلَآ أُوتِىَ مِثْلَ مَآ أُوتِىَ مُوسَىٰٓ ۚ أَوَلَمْ يَكْفُرُوا۟ بِمَآ أُوتِىَ
مُوسَىٰ مِن قَبْلُ ۖ قَالُوا۟ سِحْرَانِ تَظَٰهَرَا وَقَالُوٓا۟ إِنَّا بِكُلٍّ كَٰفِرُونَ
﴿٤٨﴾ قُلْ فَأْتُوا۟ بِكِتَٰبٍ مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ هُوَ أَهْدَىٰ مِنْهُمَآ أَتَّبِعْهُ
إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٤٩﴾ فَإِن لَّمْ يَسْتَجِيبُوا۟ لَكَ فَٱعْلَمْ
أَنَّمَا يَتَّبِعُونَ أَهْوَآءَهُمْ ۚ وَمَنْ أَضَلُّ مِمَّنِ ٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ بِغَيْرِ
هُدًى مِّنَ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٥٠﴾

(44) Kai kuma ba ka kasance a gefen (dutsen Ɗuri) na yamma ba lokacin da Muka yo wahayin manzanci zuwa ga Musa, ba ka kuma kasance cikin mahalarta wurin ba
(45) Sai dai cewa Mu Mun halicci al'ummu, sai nisan zamani ya tsawaita a gare su[1]. Kuma ba ka kasance a zaune cikin mutanen Madyana ba[2]kana karanta musu ayoyinmu, sai dai kuma Mu Mun kasance Masu aiko da (manzanni)
(46) Kuma ba ka kasance a gefen (dutsen) Ɗuri ba, lokacin da Muka kirawo (Musa), sai dai wata rahama daga Ubangijinka, don ka gargaɗi wasu mutane da mai gargaɗi bai zo musu ba gabaninka ko sa wa'azantu
(47) Kuma ba don kada wata masifa ta same su ba saboda abin da suka aikata da kansu sai su rika cewa: "Ya Ubangijinmu, ina ma da Ka aiko mana da wani manzo, da sai mu bi ayoyinka mu kuma kasance cikin muminai[3]?"
(48) To lokacin da gaskiya ta zo musu daga wajenmu sai suka ce: "Ina ma da an ba shi irin abin da aka bai wa Musa?" Yanzu ashe tun da can ba su kafirce da abin da aka bai wa Musa ba; suka ce: "Su biyun sihiri ne (wato Alkur'ani da Attaura) da suke taimakon juna?" Suka kuma ce: "Lalle mu mun kafirce da su gaba ɗaya."
(49) Ka ce (da su): "To ku zo da wani littafi daga wajen Allah wanda ya fi su nuna hanyar shiriya (wato Alkur'ani da Attaura), zan bi shi idan kun kasance masu gaskiya."
(50) To idan ba su amsa maka ba, to ka sani cewa ba abin da suke bi sai soye-soyen zukatansu kawai. Ba kuwa wanda ya fi ɓacewa kamar wanda ya bi son zuciyarsa ba tare da wata shiriya daga Allah ba. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutane azzalumai

(1) Watau al'ummun da suka zo bayan Annabi Musa ( ), sai lokaci ya tsawaita gare su har suka manta alqawarin da suka yi tsakaninsu da Allah; ilimi ya yi qaranci.

(2) Watau ba don whayin da Allah ( ) ya yi wa Manzonsa ba, da ba za san labarin abin da ya faru ga Annabi Musa ( ) ba.

(3) Watau da a ce wata azaba ta sauka a kansu saboda yawan savonsu, to da sai su ce, me ya sa Allah bai aiko musu da wani manzo ba wanda zai gargaxe su.

* وَلَقَدْ وَصَّلْنَا لَهُمُ ٱلْقَوْلَ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿٥١﴾ ٱلَّذِينَ
ءَاتَيْنَٰهُمُ ٱلْكِتَٰبَ مِن قَبْلِهِۦ هُم بِهِۦ يُؤْمِنُونَ ﴿٥٢﴾ وَإِذَا يُتْلَىٰ
عَلَيْهِمْ قَالُوٓا۟ ءَامَنَّا بِهِۦٓ إِنَّهُ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّنَآ إِنَّا كُنَّا مِن قَبْلِهِۦ
مُسْلِمِينَ ﴿٥٣﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ يُؤْتَوْنَ أَجْرَهُم مَّرَّتَيْنِ بِمَا صَبَرُوا۟ وَيَدْرَءُونَ
بِٱلْحَسَنَةِ ٱلسَّيِّئَةَ وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ يُنفِقُونَ ﴿٥٤﴾ وَإِذَا سَمِعُوا۟
ٱللَّغْوَ أَعْرَضُوا۟ عَنْهُ وَقَالُوا۟ لَنَآ أَعْمَٰلُنَا وَلَكُمْ أَعْمَٰلُكُمْ سَلَٰمٌ
عَلَيْكُمْ لَا نَبْتَغِى ٱلْجَٰهِلِينَ ﴿٥٥﴾ إِنَّكَ لَا تَهْدِى مَنْ أَحْبَبْتَ
وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَهْدِى مَن يَشَآءُ ۚ وَهُوَ أَعْلَمُ بِٱلْمُهْتَدِينَ ﴿٥٦﴾
وَقَالُوٓا۟ إِن نَّتَّبِعِ ٱلْهُدَىٰ مَعَكَ نُتَخَطَّفْ مِنْ أَرْضِنَآ ۚ أَوَلَمْ
نُمَكِّن لَّهُمْ حَرَمًا ءَامِنًا يُجْبَىٰٓ إِلَيْهِ ثَمَرَٰتُ كُلِّ شَىْءٍ رِّزْقًا
مِّن لَّدُنَّا وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٥٧﴾ وَكَمْ أَهْلَكْنَا مِن
قَرْيَةٍۭ بَطِرَتْ مَعِيشَتَهَا ۖ فَتِلْكَ مَسَٰكِنُهُمْ لَمْ تُسْكَن مِّنۢ
بَعْدِهِمْ إِلَّا قَلِيلًا ۖ وَكُنَّا نَحْنُ ٱلْوَٰرِثِينَ ﴿٥٨﴾ وَمَا كَانَ رَبُّكَ
مُهْلِكَ ٱلْقُرَىٰ حَتَّىٰ يَبْعَثَ فِىٓ أُمِّهَا رَسُولًا يَتْلُوا۟ عَلَيْهِمْ
ءَايَٰتِنَا ۚ وَمَا كُنَّا مُهْلِكِى ٱلْقُرَىٰٓ إِلَّا وَأَهْلُهَا ظَٰلِمُونَ ﴿٥٩﴾

(51) Hakika kuma Mun saukar musu da Alkur'ani (guntu-guntu) don su wa'azantu

(52) Wadanda Muka bai wa littafi a gabaninsa (Alkur'ani) (suka tsaya a kansa) su suna yin imani da shi (Alkur'ani)

(53) Idan kuma ana karanta musu (Alkur'anin) sai su ce: "Mun yi imani da shi, lalle shi gaskiya ne daga Ubangijinmu, lalle mu mun kasance Musulmi tun gabaninsa."

(54) Wadannan (su ne) za a ba su ladansu ninki biyu saboda hakurin da suka yi. Kuma suna kawar da mummunan aiki da kyakkyawa, suna kuma ciyarwa daga abin da Muka arzuta su (da shi)

(55) Idan kuma suka ji maganar banza sai su kau da kai daga gare ta, sai kuma su ce: "(Sakamakon) ayyukanmu yana gare mu, ku kuma na ayyukanku yana gare ku, kun kuɓuta daga gare mu, ba ruwanmu da wawaye!"

(56) Lalle kai ba ka iya shiryar da wanda ka so, sai dai Allah ne Yana shiryar da wanda Ya ga dama. Shi kuma ne Ya san masu shiryuwa

(57) Suka kuma ce: "Idan har Muka bi shiriya tare da kai, to za a kame mu (ribatattu) daga kasarmu[1]". (Ka ce da su): "Yanzu ashe ba Mu ne Muka ba su ikon Harami amintacce ba da ake kawo kowanne irin (nau'i) na 'ya'yan itace gare shi don arzutawa daga gare Mu?" Sai dai kuma yawancinsu ba sa sanin (haka)

(58) Kuma al'umma nawa ce Muka hallakar wadda ta butulce wa rayuwarta? To ga gidajensu can ba a zaune su ba a bayansu sai kadan[2]; Mu ne Muka kasance magadan

(59) Kuma Ubangijinka bai zamanto Mai hallakar da alkaryu ba har sai Ya aiko da manzo a cikin manyan biranensu, yana karanta musu ayoyinmu. Kuma ba Mu kasance Masu hallaka alkaryu ba sai idan mutanensu sun zama azzalumai

(1) Watau za a fincike su daga qasarsu Makka, su zama ribatattun yaqi a hannun maqiyansu.

(2) Watau daga matafiya da sukan ya da zango su zauna na xan lokaci.

وَمَآ أُوتِيتُم مِّن شَىْءٍ فَمَتَٰعُ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَزِينَتُهَا ۚ وَمَا عِندَ
ٱللَّهِ خَيْرٌ وَأَبْقَىٰٓ ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿٦٠﴾ أَفَمَن وَعَدْنَٰهُ وَعْدًا حَسَنًا
فَهُوَ لَٰقِيهِ كَمَن مَّتَّعْنَٰهُ مَتَٰعَ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ثُمَّ هُوَ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ
مِنَ ٱلْمُحْضَرِينَ ﴿٦١﴾ وَيَوْمَ يُنَادِيهِمْ فَيَقُولُ أَيْنَ شُرَكَآءِىَ
ٱلَّذِينَ كُنتُمْ تَزْعُمُونَ ﴿٦٢﴾ قَالَ ٱلَّذِينَ حَقَّ عَلَيْهِمُ ٱلْقَوْلُ رَبَّنَا
هَٰٓؤُلَآءِ ٱلَّذِينَ أَغْوَيْنَآ أَغْوَيْنَٰهُمْ كَمَا غَوَيْنَا ۖ تَبَرَّأْنَآ إِلَيْكَ ۖ
مَا كَانُوٓا۟ إِيَّانَا يَعْبُدُونَ ﴿٦٣﴾ وَقِيلَ ٱدْعُوا۟ شُرَكَآءَكُمْ فَدَعَوْهُمْ
فَلَمْ يَسْتَجِيبُوا۟ لَهُمْ وَرَأَوُا۟ ٱلْعَذَابَ ۚ لَوْ أَنَّهُمْ كَانُوا۟ يَهْتَدُونَ
﴿٦٤﴾ وَيَوْمَ يُنَادِيهِمْ فَيَقُولُ مَاذَآ أَجَبْتُمُ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿٦٥﴾
فَعَمِيَتْ عَلَيْهِمُ ٱلْأَنۢبَآءُ يَوْمَئِذٍ فَهُمْ لَا يَتَسَآءَلُونَ ﴿٦٦﴾ فَأَمَّا
مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَعَسَىٰٓ أَن يَكُونَ مِنَ ٱلْمُفْلِحِينَ
﴿٦٧﴾ وَرَبُّكَ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ وَيَخْتَارُ ۗ مَا كَانَ لَهُمُ ٱلْخِيَرَةُ ۚ سُبْحَٰنَ
ٱللَّهِ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٦٨﴾ وَرَبُّكَ يَعْلَمُ مَا تُكِنُّ
صُدُورُهُمْ وَمَا يُعْلِنُونَ ﴿٦٩﴾ وَهُوَ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ لَهُ
ٱلْحَمْدُ فِى ٱلْأُولَىٰ وَٱلْءَاخِرَةِ ۖ وَلَهُ ٱلْحُكْمُ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٧٠﴾

(60) Kuma duk irin abin da aka ba ku, to jin dadin rayuwar duniya ne da adonta. Abin da yake wurin Allah kuwa (shi) ya fi alhairi ya fi kuma wanzuwa. Yanzu ba kwa hankalta ba?

(61) Yanzu wanda Muka yi wa alkawari kyakkyawa da zai same shi, zai zama kamar wanda Muka jiyar da shi dadin rayuwar duniya, sannan kuma shi yana daga wadanda za a kai su wuta a ranar alkiyama?

(62) Kuma ka tuna ranar da (Allah) zai kirawo su sai Ya ce: "Ina abokan tarayyar nawa wadanda kuka kasance kuna riyawa?"

(63) Sai wadanda alkawarin Allah (na azaba) ya tabbata a kansu su ce: "Ya Ubangijinmu, wadannan da muka batar, mun batar da su ne kamar yadda mu ma muka bata; ba ruwanmu da kowa sai kai; don kuwa ba su kasance mu suke bauta wa ba."

(64) Kuma aka ce: "Ku kirawo abokan tarayyar naku", sannan suka kirawo su, sai ba su amsa musu ba, suka kuma ga azaba. (Suka rika burin) ina ma sun kasance shiryayyu!

(65) (Ka tuna) kuma ranar da (Allah) zai kirawo su sannan Ya ce: "Me kuka amsa wa manzanni (da shi?)"

(66) Sai abubuwan da za su fada suka bace musu a wannan ranar, don haka su ba za su iya tambayar junansu ba

(67) To amma wanda ya tuba ya kuma yi imani ya kuma yi aiki nagari, to ana fatan ya zama cikin masu samun babban rabo

(68) Kuma Ubangijinka Yana halittar abin da Ya ga dama Yana kuma zabar (abin da Ya ga dama). Ba su suke da zabi ba. Tsarki ya tabbata ga Allah kuma Ya daukaka daga abin da suke yin shirka (da shi)

(69) Kuma Ubangijinka Ya san abin da zukatansu suke boyewa da kuma abin da suke bayyanawa.

(70) Kuma Shi ne Allah, babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi; yabo ya tabbata a gare Shi a duniya da lahira; hukunci kuma nasa ne, kuma zuwa gare Shi ne kawai za a mayar da ku

قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِن جَعَلَ ٱللَّهُ عَلَيْكُمُ ٱلَّيْلَ سَرْمَدًا إِلَىٰ يَوْمِ
ٱلْقِيَـٰمَةِ مَنْ إِلَـٰهٌ غَيْرُ ٱللَّهِ يَأْتِيكُم بِضِيَآءٍ ۖ أَفَلَا تَسْمَعُونَ
﴿٧١﴾ قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِن جَعَلَ ٱللَّهُ عَلَيْكُمُ ٱلنَّهَارَ سَرْمَدًا إِلَىٰ
يَوْمِ ٱلْقِيَـٰمَةِ مَنْ إِلَـٰهٌ غَيْرُ ٱللَّهِ يَأْتِيكُم بِلَيْلٍ تَسْكُنُونَ
فِيهِ ۖ أَفَلَا تُبْصِرُونَ ﴿٧٢﴾ وَمِن رَّحْمَتِهِۦ جَعَلَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ
وَٱلنَّهَارَ لِتَسْكُنُوا۟ فِيهِ وَلِتَبْتَغُوا۟ مِن فَضْلِهِۦ وَلَعَلَّكُمْ
تَشْكُرُونَ ﴿٧٣﴾ وَيَوْمَ يُنَادِيهِمْ فَيَقُولُ أَيْنَ شُرَكَآءِىَ ٱلَّذِينَ
كُنتُمْ تَزْعُمُونَ ﴿٧٤﴾ وَنَزَعْنَا مِن كُلِّ أُمَّةٍ شَهِيدًا فَقُلْنَا
هَاتُوا۟ بُرْهَـٰنَكُمْ فَعَلِمُوٓا۟ أَنَّ ٱلْحَقَّ لِلَّهِ وَضَلَّ عَنْهُم
مَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ﴿٧٥﴾ ۞ إِنَّ قَـٰرُونَ كَانَ مِن قَوْمِ مُوسَىٰ
فَبَغَىٰ عَلَيْهِمْ ۖ وَءَاتَيْنَـٰهُ مِنَ ٱلْكُنُوزِ مَآ إِنَّ مَفَاتِحَهُۥ لَتَنُوٓأُ
بِٱلْعُصْبَةِ أُو۟لِى ٱلْقُوَّةِ إِذْ قَالَ لَهُۥ قَوْمُهُۥ لَا تَفْرَحْ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ
لَا يُحِبُّ ٱلْفَرِحِينَ ﴿٧٦﴾ وَٱبْتَغِ فِيمَآ ءَاتَىٰكَ ٱللَّهُ ٱلدَّارَ ٱلْـَٔاخِرَةَ ۖ
وَلَا تَنسَ نَصِيبَكَ مِنَ ٱلدُّنْيَا ۖ وَأَحْسِن كَمَآ أَحْسَنَ ٱللَّهُ إِلَيْكَ ۖ
وَلَا تَبْغِ ٱلْفَسَادَ فِى ٱلْأَرْضِ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿٧٧﴾

(71) Ka ce: “Ku ba ni labari, (yanzu) idan Allah Ya sanya muku dare tutur har zuwa ranar alƙiyama, wane abin bauta ne ba Allah ba zai zo muku da wani haske? To me ya sa ba kwa ji?”

(72) Ka ce: “Ku ba ni labari, (yanzu) idan Allah Ya sanya muku rana tutur har zuwa ranar alƙiyama, wane abin bauta ne ba Allah ba zai zo muku da dare da za ku samu nutsuwa a cikinsa? To me ya sa ba kwa gani?”

(73) Daga rahamarsa ne kuma Ya sanya muku dare da rana don ku samu nutsuwa a cikinsa (wato dare) kuma don ku nema daga falalarsa (da rana), don kuma ku rika yin godiya

(74) Ka kuma (tuna) ranar da (Allah) zai kirawo su, sai Ya ce: “Ina abokan tarayyar nawa waɗanda kuka kasance kuna riyawa?”

(75) Muka kuma ware wani shaida daga kowacce al’umma (watau annabinsu) sai Muka ce: “To ku kawo dalilinku (na yin tarayya da Allah).” Sai suka san cewa lalle gaskiya tana ga Allah, kuma abin da suka kasance suna ƙirƙira ya ɓace musu

(76) Lalle Karuna yana daga mutanen Musa, sai ya yi musu girman kai, Muka kuma ba shi taskokin (dukiya) wadda lalle makullansu suna yi wa tarin jama’a ƙarfafa nauyin (ɗauka), yayin da mutanensa suka ce da shi: “Kada ka yi fariya, lalle Allah ba Ya son masu fariya

(77) “Kuma ka nemi gidan lahira ta hanyar abin da Allah Ya ba ka; kada kuma ka manta rabonka na duniya; kuma ka kyautata kamar yadda Allah Ya kyautata maka, kada kuma ka nemi yin ɓarna a bayan ƙasa. Lalle Allah ba Ya son masu ɓarna.”

قَالَ إِنَّمَآ أُوتِيتُهُۥ عَلَىٰ عِلْمٍ عِندِىٓ ۚ أَوَلَمْ يَعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ قَدْ أَهْلَكَ
مِن قَبْلِهِۦ مِنَ ٱلْقُرُونِ مَنْ هُوَ أَشَدُّ مِنْهُ قُوَّةً وَأَكْثَرُ جَمْعًا ۚ
وَلَا يُسْـَٔلُ عَن ذُنُوبِهِمُ ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿٧٨﴾ فَخَرَجَ عَلَىٰ قَوْمِهِۦ
فِى زِينَتِهِۦ ۖ قَالَ ٱلَّذِينَ يُرِيدُونَ ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا يَٰلَيْتَ لَنَا
مِثْلَ مَآ أُوتِىَ قَٰرُونُ إِنَّهُۥ لَذُو حَظٍّ عَظِيمٍ ﴿٧٩﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ
أُوتُوا۟ ٱلْعِلْمَ وَيْلَكُمْ ثَوَابُ ٱللَّهِ خَيْرٌ لِّمَنْ ءَامَنَ وَعَمِلَ
صَٰلِحًا ۚ وَلَا يُلَقَّىٰهَآ إِلَّا ٱلصَّٰبِرُونَ ﴿٨٠﴾ فَخَسَفْنَا بِهِۦ
وَبِدَارِهِ ٱلْأَرْضَ فَمَا كَانَ لَهُۥ مِن فِئَةٍ يَنصُرُونَهُۥ مِن دُونِ
ٱللَّهِ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلْمُنتَصِرِينَ ﴿٨١﴾ وَأَصْبَحَ ٱلَّذِينَ تَمَنَّوْا۟
مَكَانَهُۥ بِٱلْأَمْسِ يَقُولُونَ وَيْكَأَنَّ ٱللَّهَ يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن
يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ وَيَقْدِرُ ۖ لَوْلَآ أَن مَّنَّ ٱللَّهُ عَلَيْنَا لَخَسَفَ بِنَا ۖ
وَيْكَأَنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿٨٢﴾ تِلْكَ ٱلدَّارُ ٱلْءَاخِرَةُ نَجْعَلُهَا
لِلَّذِينَ لَا يُرِيدُونَ عُلُوًّا فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا فَسَادًا ۚ وَٱلْعَٰقِبَةُ لِلْمُتَّقِينَ
﴿٨٣﴾ مَن جَآءَ بِٱلْحَسَنَةِ فَلَهُۥ خَيْرٌ مِّنْهَا ۖ وَمَن جَآءَ بِٱلسَّيِّئَةِ فَلَا
يُجْزَى ٱلَّذِينَ عَمِلُوا۟ ٱلسَّيِّـَٔاتِ إِلَّا مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٨٤﴾

(78) Ya ce: “Ai ni an ba ni ita (wato dukiyar) ta hanyar ilimin da nake da shi ne.” Shin yanzu bai sani ba ne cewa haƙiƙa Allah Ya hallaka wasu al’ummun da suke a gabaninsa waɗanda suka fi shi ƙarfi da kuma yawan tarin (dukiya)? Ba kuwa za a tambayi masu laifi game da laifinsu ba[1]

(79) Sai ya fito wa mutanensa a cikin adonsa; sai waɗanda suke burin rayuwar duniya suka ce: “Ina ma da za mu mallaki irin abin da aka bai wa Karuna? Lalle shi mai babban rabo ne.”

(80) Waɗanda kuwa aka bai wa ilimi sai suka ce:

“Kaiconku, ai ladan Allah shi ya fi alheri ga wanda ya yi imani, ya kuma yi aiki na gari. Ba kuwa wanda ake yi wa katari da shi sai masu haƙuri.”

(81) Sannan muka kifar da shi (Karuna) tare da gidansa cikin ƙasa, kuma ba shi da wata jama’a da za su taimake shi ba Allah ba, kuma bai kasance daga masu taimaka wa kawunansu ba

(82) Kuma waɗanda suka yi burin matsayinsa a jiya suka wayi gari suna cewa: “Wai, yau mun ga abin al’ajabi! Allah Yana yalwata arziki ga wanda Ya ga dama daga bayinsa, Yana kuma ƙuntatawa ga wanda Ya ga dama; ba don Allah Ya ba mu sa’a ba da mu ma Ya kifar da mu. Wai, abin mamaki, lalle kafurai ba sa rabauta!”

(83) Wancan gida na lahira Muna ba da shi ga waɗanda ba sa nufin girman kai da ɓarna a bayan ƙasa. Kyakkyawan ƙarshe kuma yana ga masu kiyaye dokokin Allah ne

(84) Duk wanda ya zo da kyakkyawan aiki, to yana da (lada) fiye da aikinsa; wanda kuma ya zo da mummunan aiki, to ba za a saka wa waɗanda suka aikata munanan ayyuka ba face daidai da abin da suka kasance suna aikatawa

(1) Watau zai hallaka su kawai ba tare da tsayawa a yi musu tambayoyi a kan laifukansu ba, ballantana a saurari hanzarinsu.

إِنَّ ٱلَّذِى فَرَضَ عَلَيْكَ ٱلْقُرْءَانَ لَرَآدُّكَ إِلَىٰ مَعَادٍ ۚ قُل رَّبِّىٓ
أَعْلَمُ مَن جَآءَ بِٱلْهُدَىٰ وَمَنْ هُوَ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٨٥﴾ وَمَا كُنتَ
تَرْجُوٓا۟ أَن يُلْقَىٰٓ إِلَيْكَ ٱلْكِتَٰبُ إِلَّا رَحْمَةً مِّن رَّبِّكَ ۖ فَلَا
تَكُونَنَّ ظَهِيرًا لِّلْكَٰفِرِينَ ﴿٨٦﴾ وَلَا يَصُدُّنَّكَ عَنْ ءَايَٰتِ
ٱللَّهِ بَعْدَ إِذْ أُنزِلَتْ إِلَيْكَ ۖ وَٱدْعُ إِلَىٰ رَبِّكَ ۖ وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ
ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٨٧﴾ وَلَا تَدْعُ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ ۘ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۚ
كُلُّ شَىْءٍ هَالِكٌ إِلَّا وَجْهَهُۥ ۚ لَهُ ٱلْحُكْمُ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٨٨﴾

سُورَةُ العَنكبُوتِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓمٓ ﴿١﴾ أَحَسِبَ ٱلنَّاسُ أَن يُتْرَكُوٓا۟ أَن يَقُولُوٓا۟ ءَامَنَّا وَهُمْ
لَا يُفْتَنُونَ ﴿٢﴾ وَلَقَدْ فَتَنَّا ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ ۖ فَلَيَعْلَمَنَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ
صَدَقُوا۟ وَلَيَعْلَمَنَّ ٱلْكَٰذِبِينَ ﴿٣﴾ أَمْ حَسِبَ ٱلَّذِينَ يَعْمَلُونَ
ٱلسَّيِّـَٔاتِ أَن يَسْبِقُونَا ۚ سَآءَ مَا يَحْكُمُونَ ﴿٤﴾ مَن كَانَ يَرْجُوا۟
لِقَآءَ ٱللَّهِ فَإِنَّ أَجَلَ ٱللَّهِ لَءَاتٍ ۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٥﴾ وَمَن
جَٰهَدَ فَإِنَّمَا يُجَٰهِدُ لِنَفْسِهِۦٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَغَنِىٌّ عَنِ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٦﴾

(85) Lalle Wanda Ya saukar maka da Alkur'ani tabbas zai mayar da kai zuwa makomarka[1]. Ka ce: "Ubangijina Shi Ya san wanda ya zo da shiriya da kuma wanda yake cikin ɓata mabayyani."

(86) Kuma ba ka kasance kana fatan a saukar maka da littafi ba, sai dai (an yi haka ne) don rahama daga Ubangijinka; to don haka kada ka zamanto mai taimakon kafirai

(87) Kuma lallai kada su hana ka (isar da) ayoyin Allah bayan an riga an saukar maka da su; kuma ka yi kira zuwa ga Ubangijinka; kuma lallai kada ka zamanto daga mushrikai

(88) Kuma kada ka bauta wa wani abin bauta daban tare da Allah. Babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. Kowane abu mai halaka ne sai Fuskarsa kawai. Hukunci (duk) nasa ne, zuwa gare Shi kuma za a mayar da ku

---

Sura Ankabut

(1) ALIF LAM MIM[2].

(2) Yanzu mutane suna tsammanin za a ƙyale su ne saboda suna cewa: "Mun yi imani," kuma ba za a fitine su ba?

(3) Haƙiƙa kuwa Mun fitini waɗanda suke gabaninsu; to tabbas kuwa Allah zai bayyana waɗanda suka yi gaskiya, lalle kuma zai bayyana maƙaryata

(4) Ko kuma waɗanda suke aikata munanan ayyuka suna tsammanin za su gagare Mu ne? Abin da suke hukuntawa ya munana

(5) Wanda ya zama yana fatan haɗuwa da Allah, to lalle lokacin (haɗuwa da) Allah tabbas mai zuwa ne. Kuma Shi ne Mai ji, Masani

(6) Duk wanda kuwa ya yi jihadi, to yana jihadin ne don kansa. Lalle Allah tabbas Mawadaci ne daga talikai

(1) Watau zai mayar da shi mahaifarsa garin Makka; ko kuma zai mayar da shi makomarsa ta qarshe watau Aljanna.

(2) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8.

وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَنُكَفِّرَنَّ عَنۡهُمۡ سَيِّـَٔاتِهِمۡ
وَلَنَجۡزِيَنَّهُمۡ أَحۡسَنَ ٱلَّذِي كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٧ وَوَصَّيۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ
بِوَٰلِدَيۡهِ حُسۡنٗاۖ وَإِن جَٰهَدَاكَ لِتُشۡرِكَ بِي مَا لَيۡسَ لَكَ بِهِۦ عِلۡمٞ
فَلَا تُطِعۡهُمَآۚ إِلَيَّ مَرۡجِعُكُمۡ فَأُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٨
وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَنُدۡخِلَنَّهُمۡ فِي ٱلصَّٰلِحِينَ
٩ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَقُولُ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ فَإِذَآ أُوذِيَ فِي ٱللَّهِ جَعَلَ
فِتۡنَةَ ٱلنَّاسِ كَعَذَابِ ٱللَّهِۖ وَلَئِن جَآءَ نَصۡرٞ مِّن رَّبِّكَ لَيَقُولُنَّ
إِنَّا كُنَّا مَعَكُمۡۚ أَوَلَيۡسَ ٱللَّهُ بِأَعۡلَمَ بِمَا فِي صُدُورِ ٱلۡعَٰلَمِينَ
١٠ وَلَيَعۡلَمَنَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَيَعۡلَمَنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ
١١ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّبِعُواْ سَبِيلَنَا
وَلۡنَحۡمِلۡ خَطَٰيَٰكُمۡ وَمَا هُم بِحَٰمِلِينَ مِنۡ خَطَٰيَٰهُم مِّن
شَيۡءٍۖ إِنَّهُمۡ لَكَٰذِبُونَ ١٢ وَلَيَحۡمِلُنَّ أَثۡقَالَهُمۡ وَأَثۡقَالٗا مَّعَ
أَثۡقَالِهِمۡۖ وَلَيُسۡـَٔلُنَّ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ عَمَّا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ
١٣ وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوۡمِهِۦ فَلَبِثَ فِيهِمۡ أَلۡفَ سَنَةٍ
إِلَّا خَمۡسِينَ عَامٗا فَأَخَذَهُمُ ٱلطُّوفَانُ وَهُمۡ ظَٰلِمُونَ ١٤

(7) Waɗanda kuma suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, tabbas za Mu kankare musu munanan ayyukansu, kuma tabbas za Mu saka musu da mafi kyan abin da suka kasance suna aikatawa

(8) Kuma Mun yi wa mutum wasiyya da kyautata wa iyayensa; idan kuma suka yaƙe ka kan ka yi shirka da Ni game da abin da ba ka da sani a kansa, to kada ka bi su. Wurina ne makomarku take kawai, sannan zan ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa

(9) Waɗanda kuma suka yi imani suka yi ayyuka nagari tabbas za Mu shigar da su cikin salihai

(10) Kuma cikin mutane akwai mai cewa: "Mun yi imani da Allah," to idan aka cuce shi a kan hanyar Allah sai yakan ɗauki fitinar mutane kamar azabar Allah, lalle kuwa idan wata nasara ta zo daga Ubangijinka, tabbas zai riƙa cewa: "Lalle mu mun kasance tare da ku." Yanzu Allah ba Shi Ya fi kowa sanin abin da ke cikin zukatan talikai ba?

(11) Tabbas kuma Allah zai bayyana waɗanda suka yi imani, kuma tabbas zai bayyana munafukai

(12) Kuma waɗanda suka kafirta suka ce da waɗanda suka yi imani: "Ku bi tafarkinmu, (mu) lalle za mu ɗauke muku laifuffukanku," alhali kuwa su ba za su iya ɗauke wani abu na laifuffukansu ba; lalle su dai tabbas maƙaryata ne

(13) Tabbas kuma za su ɗauki zunubansu da kuma wasu zunuban tare da zunubansu[1]; kuma tabbas za a tambaye su a ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna ƙirƙira

(14) Kuma haƙiƙa Mun aiko Nuhu zuwa ga mutanensa, sai ya zauna cikinsu shekara dubu ba hamsin, sai (ruwan) Ɗufana ya ci su, alhalin suna azzalumai

(1) Watau tare da zunuban waxanda suka yaudara suka vatar da su, ba kuma tare da an rage zunuban mabiyansu ba.

فَأَنجَيْنَٰهُ وَأَصْحَٰبَ ٱلسَّفِينَةِ وَجَعَلْنَٰهَآ ءَايَةً لِّلْعَٰلَمِينَ
(١٥) وَإِبْرَٰهِيمَ إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ وَٱتَّقُوهُ ۖ ذَٰلِكُمْ
خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ (١٦) إِنَّمَا تَعْبُدُونَ مِن
دُونِ ٱللَّهِ أَوْثَٰنًا وَتَخْلُقُونَ إِفْكًا ۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَعْبُدُونَ مِن
دُونِ ٱللَّهِ لَا يَمْلِكُونَ لَكُمْ رِزْقًا فَٱبْتَغُوا۟ عِندَ ٱللَّهِ ٱلرِّزْقَ
وَٱعْبُدُوهُ وَٱشْكُرُوا۟ لَهُۥ ۖ إِلَيْهِ تُرْجَعُونَ (١٧) وَإِن تُكَذِّبُوا۟
فَقَدْ كَذَّبَ أُمَمٌ مِّن قَبْلِكُمْ ۖ وَمَا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلْبَلَٰغُ
ٱلْمُبِينُ (١٨) أَوَلَمْ يَرَوْا۟ كَيْفَ يُبْدِئُ ٱللَّهُ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ
يُعِيدُهُۥ ۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ (١٩) قُلْ سِيرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ
فَٱنظُرُوا۟ كَيْفَ بَدَأَ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ ٱللَّهُ يُنشِئُ ٱلنَّشْأَةَ ٱلْءَاخِرَةَ ۚ
إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ (٢٠) يُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ وَيَرْحَمُ
مَن يَشَآءُ ۖ وَإِلَيْهِ تُقْلَبُونَ (٢١) وَمَآ أَنتُم بِمُعْجِزِينَ فِى
ٱلْأَرْضِ وَلَا فِى ٱلسَّمَآءِ ۖ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن
وَلِىٍّ وَلَا نَصِيرٍ (٢٢) وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَلِقَآئِهِۦٓ
أُو۟لَٰٓئِكَ يَئِسُوا۟ مِن رَّحْمَتِى وَأُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ (٢٣)

(15) Sai Muka tserar da shi tare da mutanen jirgin ruwa, Muka kuma sanya shi (jirgin) aya ga talikai

(16) Kuma (ka tuna) Ibrahimu lokacin da ya ce da mutanensa: "Ku bauta wa Allah, kuma ku kiyaye dokokinsa, wannan shi ya fi muku alheri in kun kasance kun san (haka)

(17) Lalle abin da kuke bauta wa ba Allah ba gumaka ne kawai, kuna kuma ƙirƙirar ƙarya ne[1]. Lalle waɗanda kuke bauta wa ba Allah ba, ba su mallaki wani arziki ba gare ku, sai ku nemi arziki a wurin Allah, kuma ku bauta masa, ku kuma gode masa; gare Shi ne kawai za a mayar da ku

(18) Idan kuma kuka ƙaryata, to haƙiƙa da ma wasu al'ummun da suke gabaninku sun ƙaryata; ba abin da yake kan Manzo sai isar da saƙo mabayyani

(19) Yanzu ba su ga yadda Allah Yake farar halitta ba, sannan Shi ne kuma zai mayar da ita? Lalle wannan mai sauƙi ne a wurin Allah

(20) Ka ce: "Ku yi tafiya a bayan ƙasa sai ku duba ku ga yadda Allah Ya fari halittu. Sannan Allah ne zai sake samar da su samarwar ƙarshe. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai

(21) "Yana azabtar da wanda Ya ga dama, Yana kuma jin ƙan wanda Ya ga dama; kuma wurinsa kawai za a mayar da ku

(22) "Kuma ku ba za ku gagara ba a ƙasa ko kuma a sama; kuma ba ku da wani majiɓinci ko mataimaki in ba Allah ba."

(23) Waɗanda kuma suka kafirce wa ayoyin Allah da kuma gamuwa da Shi, waɗannan sun ɗebe ƙauna daga rahamata, kuma waɗannan suna da azaba mai raɗadi

(1) Domin su ne suke sassaqa su da hannayensu suke kuma sanya musu sunaye sannan su bauta musu.

فَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُوا۟ ٱقْتُلُوهُ أَوْ حَرِّقُوهُ
فَأَنجَىٰهُ ٱللَّهُ مِنَ ٱلنَّارِ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ
﴿٢٤﴾ وَقَالَ إِنَّمَا ٱتَّخَذْتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ أَوْثَٰنًا مَّوَدَّةَ بَيْنِكُمْ
فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ ثُمَّ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يَكْفُرُ بَعْضُكُم
بِبَعْضٍ وَيَلْعَنُ بَعْضُكُم بَعْضًا وَمَأْوَىٰكُمُ ٱلنَّارُ
وَمَا لَكُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿٢٥﴾ فَـَٔامَنَ لَهُۥ لُوطٌ ۘ وَقَالَ
إِنِّى مُهَاجِرٌ إِلَىٰ رَبِّىٓ ۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٢٦﴾
وَوَهَبْنَا لَهُۥٓ إِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ وَجَعَلْنَا فِى ذُرِّيَّتِهِ
ٱلنُّبُوَّةَ وَٱلْكِتَٰبَ وَءَاتَيْنَٰهُ أَجْرَهُۥ فِى ٱلدُّنْيَا ۖ وَإِنَّهُۥ
فِى ٱلْءَاخِرَةِ لَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿٢٧﴾ وَلُوطًا إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦٓ
إِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ ٱلْفَٰحِشَةَ مَا سَبَقَكُم بِهَا مِنْ أَحَدٍ
مِّنَ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٢٨﴾ أَئِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ ٱلرِّجَالَ وَتَقْطَعُونَ
ٱلسَّبِيلَ وَتَأْتُونَ فِى نَادِيكُمُ ٱلْمُنكَرَ ۖ فَمَا كَانَ جَوَابَ
قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُوا۟ ٱئْتِنَا بِعَذَابِ ٱللَّهِ إِن كُنتَ مِنَ
ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿٢٩﴾ قَالَ رَبِّ ٱنصُرْنِى عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿٣٠﴾

(24) To ba wani jawabi da ya fito daga bakin mutanensa sai cewa da suka yi: “Ku kashe shi ko kuma ku ƙone shi!” Sai Allah Ya tserar da shi daga wutar. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutanen da suka yi imani

(25) Kuma ya ce (da su): “Lalle ba abin da kuka rika wanin Allah sai gumaka kawai don ƙauna da take tsakaninku a rayuwar duniya; sannan ranar alƙiyama wasunku za su kafirce wa wasu, kuma wasunku za su la’anci wasu, makomarku kuma wuta ce, ba ku da kuwa wasu mataimaka.”

(26) Sai Luɗu ya yi imani da shi. (Sai Ibrahimu) kuma ya ce: “Lalle ni mai yin hijira ne zuwa ga Ubangijina; lalle Shi Mabuwayi ne, Mai hikima.”

(27) Muka kuma yi masa baiwa da (ɗansa) Is’haƙa da kuma (jikansa) Ya’ɑkubu, Muka kuma sanya annabta da littafi a cikin zuriyarsa, Muka kuma ba shi ladansa a duniya; kuma lalle shi a lahira tabbas yana cikin salihai

(28) Kuma (ka tuna) Luɗu lokacin da ya ce da mutanensa: “Lalle ku kuna zaike wa mummunan aiki wanda ba wani mutum guda daga talikai da ya rigaye ku (aikata) shi

(29) “Yanzu kwa riƙa zaike wa maza, ku kuma riƙa tsare hanya (kuna yin fashi), kuma kuna aikata abin ƙi a cikin majalisarku[1]?” Ba wani jawabi da ya fito daga bakin mutanensa sai cewa suka yi: “To ka zo mana da azabar Allah idan ka kasance cikin masu gaskiya.”

(30) (Sai Luɗu) ya ce: “Ya Ubangijina, Ka taimake ni kan mutanen nan maɓarnata.”

(1) Watau kamar nuna tsiraici da cutar da masu wucewa a hanya da maganganunsu da ayyukansu.

وَلَمَّا جَآءَتْ رُسُلُنَآ إِبْرَٰهِيمَ بِٱلْبُشْرَىٰ قَالُوٓا۟ إِنَّا مُهْلِكُوٓا۟
أَهْلِ هَٰذِهِ ٱلْقَرْيَةِ ۖ إِنَّ أَهْلَهَا كَانُوا۟ ظَٰلِمِينَ ﴿٣١﴾
قَالَ إِنَّ فِيهَا لُوطًا ۚ قَالُوا۟ نَحْنُ أَعْلَمُ بِمَن فِيهَا ۖ لَنُنَجِّيَنَّهُۥ
وَأَهْلَهُۥٓ إِلَّا ٱمْرَأَتَهُۥ كَانَتْ مِنَ ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿٣٢﴾ وَلَمَّآ
أَن جَآءَتْ رُسُلُنَا لُوطًا سِىٓءَ بِهِمْ وَضَاقَ بِهِمْ ذَرْعًا ۖ
وَقَالُوا۟ لَا تَخَفْ وَلَا تَحْزَنْ ۖ إِنَّا مُنَجُّوكَ وَأَهْلَكَ إِلَّا
ٱمْرَأَتَكَ كَانَتْ مِنَ ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿٣٣﴾ إِنَّا مُنزِلُونَ عَلَىٰٓ أَهْلِ
هَٰذِهِ ٱلْقَرْيَةِ رِجْزًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ بِمَا كَانُوا۟ يَفْسُقُونَ
﴿٣٤﴾ وَلَقَد تَّرَكْنَا مِنْهَآ ءَايَةًۢ بَيِّنَةً لِّقَوْمٍ يَعْقِلُونَ
﴿٣٥﴾ وَإِلَىٰ مَدْيَنَ أَخَاهُمْ شُعَيْبًا فَقَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ
وَٱرْجُوا۟ ٱلْيَوْمَ ٱلْءَاخِرَ وَلَا تَعْثَوْا۟ فِى ٱلْأَرْضِ مُفْسِدِينَ
﴿٣٦﴾ فَكَذَّبُوهُ فَأَخَذَتْهُمُ ٱلرَّجْفَةُ فَأَصْبَحُوا۟ فِى دَارِهِمْ
جَٰثِمِينَ ﴿٣٧﴾ وَعَادًا وَثَمُودَا۟ وَقَد تَّبَيَّنَ لَكُم
مِّن مَّسَٰكِنِهِمْ ۖ وَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيْطَٰنُ أَعْمَٰلَهُمْ
فَصَدَّهُمْ عَنِ ٱلسَّبِيلِ وَكَانُوا۟ مُسْتَبْصِرِينَ ﴿٣٨﴾

(31) Lokacin kuwa da manzanninmu suka zo wa Ibrahimu da albishir[1], sai suka ce: "Lalle mu masu hallaka mutanen wannan alkaryar ne, lalle mutanenta sun kasance azzalumai."

(32) Sai (Ibrahimu) ya ce: "Lalle Luɗu yana cikinta". Sai suka ce: "Mu muka fi sanin waɗanda suke cikinta; tabbas za mu tserar da shi tare da iyalinsa, sai matarsa kawai da ta kasance cikin waɗanda za su yi saura (a hallaka su tare)"

(33) Lokacin kuma da manzanninmu suka zo wa Luɗu, sai ya yi baƙin ciki da zuwansu, zuciyarsa kuma ta ƙuntata saboda su[2], sai suka ce da shi: "Kada ka ji tsoro, kuma kada ka damu; lalle mu masu tserar da kai ne tare da iyalinka, sai matarka kawai da ta kasance cikin waɗanda za su yi saura (a hallaka su tare)

(34) "Lalle mu masu saukar da azaba ce daga sama a kan mutanen wannan alƙaryar saboda abin da suka kasance suna aikatawa na fasiƙanci."

(35) Kuma haƙiƙa Mu mun bar aya bayyananniya game da ita (alƙaryar) ga mutanen da suke hankalta

(36) Mun kuma (aika wa mutanen) Madyana ɗan'uwansu Shu'aibu, sai ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, kuma ku yi fatan (kyakkyawan samakon) ranar lahira, kada kuma ku rika yaɗa ɓarna a bayan ƙasa."

(37) Sai suka ƙaryata shi, sai girgizar ƙasa ta kama su, suka wayi gari duddurƙushe (matattu) cikin gidajensu

(38) Kuma (Mun hallaka) Adawa da Samudawa, haƙiƙa (abin da ya faru a gare su) ya bayyana gare ku a fili a gidajensu; kuma Shaiɗan ya ƙawata musu ayyukansu, sai ya kange su daga hanya (madaidaiciya), sun kuma kasance masu gani da basirarsu (amma suka zaɓi ɓata)

(1) Albishir na samun haihuwar xansa Ishaq ( ) da kuma jikansa Ya'aqub ( ).

(2) Domin jiye musu tsoron mugun halin mutanensa musamman saboda mala'ikun sun zo a cikin kamanni na mutane maza.

وَقَٰرُونَ وَفِرْعَوْنَ وَهَٰمَٰنَ ۖ وَلَقَدْ جَآءَهُم مُّوسَىٰ بِٱلْبَيِّنَٰتِ
فَٱسْتَكْبَرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا كَانُوا۟ سَٰبِقِينَ ﴿٣٩﴾
فَكُلًّا أَخَذْنَا بِذَنۢبِهِۦ ۖ فَمِنْهُم مَّنْ أَرْسَلْنَا عَلَيْهِ حَاصِبًا
وَمِنْهُم مَّنْ أَخَذَتْهُ ٱلصَّيْحَةُ وَمِنْهُم مَّنْ خَسَفْنَا بِهِ
ٱلْأَرْضَ وَمِنْهُم مَّنْ أَغْرَقْنَا ۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظْلِمَهُمْ
وَلَٰكِن كَانُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿٤٠﴾ مَثَلُ ٱلَّذِينَ
ٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَوْلِيَآءَ كَمَثَلِ ٱلْعَنكَبُوتِ
ٱتَّخَذَتْ بَيْتًا ۖ وَإِنَّ أَوْهَنَ ٱلْبُيُوتِ لَبَيْتُ ٱلْعَنكَبُوتِ ۚ
لَوْ كَانُوا۟ يَعْلَمُونَ ﴿٤١﴾ إِنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا يَدْعُونَ مِن
دُونِهِۦ مِن شَىْءٍ ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٤٢﴾ وَتِلْكَ
ٱلْأَمْثَٰلُ نَضْرِبُهَا لِلنَّاسِ ۖ وَمَا يَعْقِلُهَآ إِلَّا ٱلْعَٰلِمُونَ
﴿٤٣﴾ خَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ بِٱلْحَقِّ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ
لَءَايَةً لِّلْمُؤْمِنِينَ ﴿٤٤﴾ ٱتْلُ مَآ أُوحِىَ إِلَيْكَ مِنَ ٱلْكِتَٰبِ
وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ ۖ إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ تَنْهَىٰ عَنِ ٱلْفَحْشَآءِ
وَٱلْمُنكَرِ ۗ وَلَذِكْرُ ٱللَّهِ أَكْبَرُ ۗ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ مَا تَصْنَعُونَ ﴿٤٥﴾



(39) Kuma (Mun hallaka) Karuna da Fir'auna da Hamana; hakika kuma Musa ya zo musu da hujjoji bayyanannu, sai suka yi girman kai a bayan ƙasa, kuma ba su kasance masu guje wa (azaba) ba


(40) Kowanne (cikin al'ummun da suka gabata) Mun kama shi da laifinsa; daga cikinsu akwai waɗanda Muka aiko wa da duwatsu, akwai kuma waɗanda tsawa ta kama su, kuma daga cikinsu akwai waɗanda Muka kifar da su cikin ƙasa, akwai kuma daga cikinsu waɗanda Muka nutsar a ruwa. Allah kuma bai kasance Yana zaluntar su ba, sai dai kawai kawunansu suke zalunta

(41) Misalin waɗanda suka riƙi wasu iyayen giji ba Allah ba, kamar misalin gizo-gizo ne da ya saƙa gida; hakika kuwa lalle gidan gizo-gizo shi ya fi kowanne gida rauni, da sun kasance suna sanin (haka)(42) Lalle Allah Yana sane da kowane abu da suke bauta wa wanda ba Shi ba. Kuma Shi ne Mabuwayi, Mai hikima

(43) Waɗancan misalan Muna ba da su ne ga mutane; ba kuwa wanda yake hankaltar su sai malamai kawai

(44) Allah Ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya ga muminai

(45) Ka karanta abin da ake yi maka wahayinsa na Alƙur'ani, ka kuma tsai da salla; lalle salla tana hana alfasha da kuma abin ƙi. Kuma tabbas ambaton Allah shi ne mafi girma. Kuma Allah Yana sane da abin da kuke aikatawa


* وَلَا تُجَٰدِلُوٓاْ أَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ إِلَّا بِٱلَّتِي هِيَ أَحۡسَنُ إِلَّا
ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنۡهُمۡۖ وَقُولُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱلَّذِيٓ أُنزِلَ إِلَيۡنَا وَأُنزِلَ
إِلَيۡكُمۡ وَإِلَٰهُنَا وَإِلَٰهُكُمۡ وَٰحِدٞ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ
٤٦ وَكَذَٰلِكَ أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَۚ فَٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ
ٱلۡكِتَٰبَ يُؤۡمِنُونَ بِهِۦۖ وَمِنۡ هَٰٓؤُلَآءِ مَن يُؤۡمِنُ بِهِۦۚ وَمَا
يَجۡحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَّا ٱلۡكَٰفِرُونَ ٤٧ وَمَا كُنتَ تَتۡلُواْ مِن
قَبۡلِهِۦ مِن كِتَٰبٖ وَلَا تَخُطُّهُۥ بِيَمِينِكَۖ إِذٗا لَّٱرۡتَابَ
ٱلۡمُبۡطِلُونَ ٤٨ بَلۡ هُوَ ءَايَٰتُۢ بَيِّنَٰتٞ فِي صُدُورِ ٱلَّذِينَ
أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَۚ وَمَا يَجۡحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَّا ٱلظَّٰلِمُونَ ٤٩ وَقَالُواْ
لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡهِ ءَايَٰتٞ مِّن رَّبِّهِۦۚ قُلۡ إِنَّمَا ٱلۡأٓيَٰتُ عِندَ ٱللَّهِ
وَإِنَّمَآ أَنَا۠ نَذِيرٞ مُّبِينٌ ٥٠ أَوَلَمۡ يَكۡفِهِمۡ أَنَّآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكَ
ٱلۡكِتَٰبَ يُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَرَحۡمَةٗ وَذِكۡرَىٰ
لِقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٥١ قُلۡ كَفَىٰ بِٱللَّهِ بَيۡنِي وَبَيۡنَكُمۡ
شَهِيدٗاۖ يَعۡلَمُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
بِٱلۡبَٰطِلِ وَكَفَرُواْ بِٱللَّهِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٥٢

(46) Kuma kada ku yi jayayya da ma'abota littafi (Yahudu da Nasara) sai ta hanyar da ta fi kyau, sai dai waɗanda suka yi zalunci daga cikinsu; kuma ku ce: "Mun yi imani da abin da aka saukar mana da kuma abin da aka saukar muku, kuma Abin bautarmu da Abin bautarku Daya ne, kuma mu masu miƙa wuya ne gare Shi."
(47) Kamar haka kuma Muka saukar maka da Alƙur'ani. To waɗanda Muka bai wa littafi (a gabaninka) suna imani da shi; daga waɗannan kuma (wato mutanen Makka) akwai wanda yake imani da shi. Ba kuwa mai musun ayoyinmu sai kafirai
(48) Ba ka zamanto kuma kana karanta wani littafi kafinsa ba (wato Alkur'ani), kuma ba ka rubuta shi da hannun damanka; da kuwa haka ya faru, to da sai masu ƙaryatawa su shiga kokwanto
(49) A'a, shi dai (Alƙur'ani) ayoyi ne bayyanannu (da suke) cikin zukatan waɗanda aka bai wa ilimi. Ba kuwa mai yin musun ayoyinmu sai azzalumai
(50) Suka kuma ce: "Me ya hana a saukar masa da wasu ayoyi daga Ubangijinsa?" Ka ce (da su): "Ayoyi suna wurin Allah ne kawai, ni kuma ba kowa ba ne face mai gargaɗi, mai bayyana (gargaɗin)."
(51) Yanzu bai ishe su ba cewa, Mun saukar maka da Littafi da ake karanta musu shi? Lalle a game da wannan tabbas akwai rahama da kuma tunatarwa ga mutanen da suke yin imani
(52) Ka ce (da su): "Allah Ya isa shaida tsakanina da ku; Yana sane da abin da yake cikin sammai da ƙasa. Waɗanda kuwa suka yi imani da ƙarya suka kuma kafirce wa Allah, waɗannan su ne asararru."

وَيَسْتَعْجِلُونَكَ بِٱلْعَذَابِ وَلَوْلَآ أَجَلٌ مُّسَمًّى لَّجَآءَهُمُ ٱلْعَذَابُ ۚ
وَلَيَأْتِيَنَّهُم بَغْتَةً وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿٥٣﴾ يَسْتَعْجِلُونَكَ بِٱلْعَذَابِ
وَإِنَّ جَهَنَّمَ لَمُحِيطَةٌۢ بِٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٥٤﴾ يَوْمَ يَغْشَىٰهُمُ ٱلْعَذَابُ
مِن فَوْقِهِمْ وَمِن تَحْتِ أَرْجُلِهِمْ وَيَقُولُ ذُوقُوا۟ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ
﴿٥٥﴾ يَٰعِبَادِيَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِنَّ أَرْضِى وَٰسِعَةٌ فَإِيَّٰىَ فَٱعْبُدُونِ
﴿٥٦﴾ كُلُّ نَفْسٍ ذَآئِقَةُ ٱلْمَوْتِ ۖ ثُمَّ إِلَيْنَا تُرْجَعُونَ ﴿٥٧﴾ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَنُبَوِّئَنَّهُم مِّنَ ٱلْجَنَّةِ غُرَفًا تَجْرِى
مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۚ نِعْمَ أَجْرُ ٱلْعَٰمِلِينَ ﴿٥٨﴾ ٱلَّذِينَ
صَبَرُوا۟ وَعَلَىٰ رَبِّهِمْ يَتَوَكَّلُونَ ﴿٥٩﴾ وَكَأَيِّن مِّن دَآبَّةٍ لَّا تَحْمِلُ
رِزْقَهَا ٱللَّهُ يَرْزُقُهَا وَإِيَّاكُمْ ۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٦٠﴾ وَلَئِن
سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَسَخَّرَ ٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ
لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ۖ فَأَنَّىٰ يُؤْفَكُونَ ﴿٦١﴾ ٱللَّهُ يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ مِنْ
عِبَادِهِۦ وَيَقْدِرُ لَهُۥٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿٦٢﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم
مَّن نَّزَّلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَحْيَا بِهِ ٱلْأَرْضَ مِنۢ بَعْدِ مَوْتِهَا
لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ۚ قُلِ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ۚ بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْقِلُونَ ﴿٦٣﴾

(53) Suna kuma neman ka da ka gaggauto musu da azaba. Ba don kuwa akwai lokaci na musamman (da aka tanada) ba, tabbas da azabar ta zo musu, kuma tabbas da za ta zo musu ne ba zato ba tsammani, alhali ba su sani ba

(54) Suna (kuma) neman ka da ka gaggauto musu da azaba, alhali kuwa Jahannama tabbas mai kewaye kafirai ce

(55) A ranar da azaba za ta lulluɓe su ta samansu da ta ƙarƙashin ƙafafuwansu, kuma (Allah) Ya ce (da su): "Ku ɗanɗani abin da kuka kasance kuna aikatawa."

(56) Ya ku bayina waɗanda suka yi imani, lalle ƙasata yalwatacciya ce, to Ni kaɗai sai ku bauta Mini

(57) Kowanne rai zai ɗanɗani mutuwa; sannan wurinmu za a mayar da ku

(58) Waɗanda kuma suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, lallai za Mu zaunar da su cikin manya-manyan gidaje a Aljanna (waɗanda) ƙoramu za su riƙa gudana ta ƙarƙashinsu suna madawwama a cikinsu. Madalla da ladan masu aiki (nagari)

(59) (Su ne) waɗanda suka yi haƙuri, kuma ga Ubangijinsu kawai suke dogara

(60) Sau tari ga dabba nan da ba za ta iya ɗaukar arzikinta ba, Allah ne Yake arzuta ta har da ku. Shi ne Mai ji, Masani

(61) Tabbas da za ka tambaye su: "Wane ne ya halicci sammai da ƙasa, ya kuma hore rana da wata?" To tabbas za su ce: "Allah ne." To ta yaya ake karkatar da su (daga kaɗaita Shi)?

(62) Allah Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama daga bayinsa, Ya kuma ƙuntata masa. Lalle Allah Masanin komai ne

(63) Kuma tabbas da za ka tambaye su: "Wane ne ya saukar da ruwa daga sama, sai ya raya ƙasa da shi bayan mutuwarta?" Lalle za su ce: "Allah ne." Ka ce (da su): "Alhamdu Lillahi." A'a, yawancinsu dai ba sa hankalta

وَمَا هَٰذِهِ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَآ إِلَّا لَهْوٌ وَلَعِبٌ ۚ وَإِنَّ ٱلدَّارَ ٱلْءَاخِرَةَ لَهِىَ
ٱلْحَيَوَانُ ۚ لَوْ كَانُوا۟ يَعْلَمُونَ ﴿٦٤﴾ فَإِذَا رَكِبُوا۟ فِى ٱلْفُلْكِ دَعَوُا۟ ٱللَّهَ
مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ فَلَمَّا نَجَّىٰهُمْ إِلَى ٱلْبَرِّ إِذَا هُمْ يُشْرِكُونَ ﴿٦٥﴾
لِيَكْفُرُوا۟ بِمَآ ءَاتَيْنَٰهُمْ وَلِيَتَمَتَّعُوا۟ ۖ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ﴿٦٦﴾
أَوَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّا جَعَلْنَا حَرَمًا ءَامِنًا وَيُتَخَطَّفُ ٱلنَّاسُ مِنْ
حَوْلِهِمْ ۚ أَفَبِٱلْبَٰطِلِ يُؤْمِنُونَ وَبِنِعْمَةِ ٱللَّهِ يَكْفُرُونَ ﴿٦٧﴾
وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوْ كَذَّبَ بِٱلْحَقِّ لَمَّا جَآءَهُۥ ۚ
أَلَيْسَ فِى جَهَنَّمَ مَثْوًى لِّلْكَٰفِرِينَ ﴿٦٨﴾ وَٱلَّذِينَ جَٰهَدُوا۟
فِينَا لَنَهْدِيَنَّهُمْ سُبُلَنَا ۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَمَعَ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٦٩﴾

سُورَةُ الرُّومِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓمٓ ﴿١﴾ غُلِبَتِ ٱلرُّومُ ﴿٢﴾ فِىٓ أَدْنَى ٱلْأَرْضِ وَهُم مِّنۢ
بَعْدِ غَلَبِهِمْ سَيَغْلِبُونَ ﴿٣﴾ فِى بِضْعِ سِنِينَ ۗ لِلَّهِ ٱلْأَمْرُ
مِن قَبْلُ وَمِنۢ بَعْدُ ۚ وَيَوْمَئِذٍ يَفْرَحُ ٱلْمُؤْمِنُونَ ﴿٤﴾
بِنَصْرِ ٱللَّهِ ۚ يَنصُرُ مَن يَشَآءُ ۖ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٥﴾

(64) Kuma wannan rayuwar duniya ba komai ba ce face sharholiya da wasa. Kuma lalle (rayuwar) gidan lahira ita ce rayuwa, in da sun kasance sun sani

(65) To idan suka hau jiragen ruwa sukan roki Allah suna masu tsantsanta addini a gare Shi; to lokacin da Ya tserar da su zuwa tudu sai ga su suna yin shirka

(66) Don su kafirce wa abin da Muka ba su, kuma don su ji dadi; to da sannu za su sani

(67) Yanzu ba su ga cewa, Mu Muka sanya musu Harami amintacce ba, alhali kuwa ana ta fauce mutane a kewayensu[1]? Shin yanzu sa rika yin imani da karya su kuma rika kafirce wa ni'imar Allah?

(68) Wane ne ya fi zalunci kamar wanda ya kaga wa Allah karya ko kuma ya karyata gaskiya lokacin da ta zo masa? Yanzu ashe babu mazaunar kafirai a cikin Jahannama?

(69) Wadanda kuma suka yi jihadi saboda Mu to tabbas za Mu shiryar da su hanyoyinmu[2], kuma lalle Allah Yana tare da masu kyautatawa

Sura Rum

(1) ALIF LAM MIM[3].

(2) An yi galaba a kan Rumawa[4]

(3) A kasa mafi kusa (da su), su kuma da sannu za su yi galaba (a kan Farisa) bayan galabar da aka yi a kansu

(4) A cikin 'yan tsirarun shekarun (da ba su kai goma ba). Al'amari a da can da nan gaba na Allah ne. A wannan ranar ne muminai za su yi farin ciki

(5) Da samun nasar Allah (a kan Farisa). Shi Yake taimakon wanda Ya ga dama; domin kuwa Shi ne Mabuwayi, Mai rahama

(1) Watau ana ta kai musu hare-hare ana kashe su, ana kama su ribatattun yaqi, a mayar da su bayi.

(2) Watau hanyoyin Allah na alheri, su samu dacewa da bin tafarki madaidaici.

(3) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8.

(4) Watau Farisawa masu bautar wuta sun yi galaba a kan Rumawa masu bin addinin Annabi Isa ( ) a wani yaqi da ya varke tsakaninsu.

وَعْدَ ٱللَّهِ ۖ لَا يُخْلِفُ ٱللَّهُ وَعْدَهُۥ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ
٦ يَعْلَمُونَ ظَٰهِرًا مِّنَ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَهُمْ عَنِ ٱلْءَاخِرَةِ هُمْ
غَٰفِلُونَ ٧ أَوَلَمْ يَتَفَكَّرُوا۟ فِىٓ أَنفُسِهِم ۗ مَّا خَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَآ إِلَّا بِٱلْحَقِّ وَأَجَلٍ مُّسَمًّى ۗ وَإِنَّ كَثِيرًا
مِّنَ ٱلنَّاسِ بِلِقَآئِ رَبِّهِمْ لَكَٰفِرُونَ ٨ أَوَلَمْ يَسِيرُوا۟ فِى
ٱلْأَرْضِ فَيَنظُرُوا۟ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ ۚ كَانُوٓا۟
أَشَدَّ مِنْهُمْ قُوَّةً وَأَثَارُوا۟ ٱلْأَرْضَ وَعَمَرُوهَآ أَكْثَرَ مِمَّا
عَمَرُوهَا وَجَآءَتْهُمْ رُسُلُهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ ۖ فَمَا كَانَ ٱللَّهُ
لِيَظْلِمَهُمْ وَلَٰكِن كَانُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ٩ ثُمَّ كَانَ
عَٰقِبَةَ ٱلَّذِينَ أَسَٰٓـُٔوا۟ ٱلسُّوٓأَىٰٓ أَن كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَكَانُوا۟
بِهَا يَسْتَهْزِءُونَ ١٠ ٱللَّهُ يَبْدَؤُا۟ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ ثُمَّ إِلَيْهِ تُرْجَعُونَ
١١ وَيَوْمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يُبْلِسُ ٱلْمُجْرِمُونَ ١٢ وَلَمْ يَكُن لَّهُم مِّن
شُرَكَآئِهِمْ شُفَعَٰٓؤُا۟ وَكَانُوا۟ بِشُرَكَآئِهِمْ كَٰفِرِينَ
١٣ وَيَوْمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يَوْمَئِذٍ يَتَفَرَّقُونَ ١٤ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَهُمْ فِى رَوْضَةٍ يُحْبَرُونَ ١٥

(6) (Wannan ya kasance) alƙawarin Allah ne; Allah ba Ya saɓa alƙawarinsa, sai dai kuma yawancin mutane ba su san (haka) ba

(7) Suna sanin abin da yake a sarari na rayuwar duniya ne, alhali kuwa su gafalallu ne game da lahira

(8) Yanzu ba su yi tunani a kan kansu ba? Allah bai halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu ba sai da gaskiya kuma (ya yi su zuwa) lokaci ƙayyadajje. Lalle mafi yawan mutane masu kafircewa ne da haɗuwa da Ubangijinsu

(9) Shin ba za su yi tafiya a bayan ƙasa ba su ga yadda ƙarshen waɗanda suka gabace su ya zama? Sun kasance sun fi su tsananin ƙarfi, sun kuma tona ƙasa suka kuma raya ta fiye da yadda su (mutanen Makka) suka raya ta, kuma manzanninsu sun zo musu da (ayoyi) bayyanannu; to Allah bai kasance Mai zaluntar su ba, sai dai su ne suka kasance suna zaluntar kawunansu

(10) Sannan kuma ƙarshen waɗanda suka munana (ayyukansu) ya kasance mummunan (sakamako), don sun ƙaryata ayoyin Allah, kuma sun kasance suna yin izgili gare su

(11) Allah ne Yake farar halitta sannan Ya dawo da ita (bayan mutuwa), sannan kuma gare Shi za a komar da ku

(12) Kuma ranar da alƙiyama za ta tashi, a wannan ranar ne masu manyan laifuka (kafirai) za su yanke ƙauna daga rahama

(13) Daga abokan tarayyar tasu kuwa ba su da wasu masu ceton su, za su ma kasance masu kafirce wa abokan tarayyar tasu

(14) Kuma ranar da alƙiyama za ta tashi, a wannan ranar ne (mutane) za su rarrabu[1]

(15) To amma waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, to su kam suna cikin dausayin (Aljanna) ana faranta musu rai

(1) Watau qungiya biyu, qungiyar muminai masu shiga Aljanna da ta kafirai masu shiga wuta.

وَأَمَّا ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَلِقَآءِ ٱلۡأٓخِرَةِ
فَأُوْلَٰٓئِكَ فِي ٱلۡعَذَابِ مُحۡضَرُونَ ﴿١٦﴾ فَسُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ حِينَ تُمۡسُونَ
وَحِينَ تُصۡبِحُونَ ﴿١٧﴾ وَلَهُ ٱلۡحَمۡدُ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ
وَعَشِيّٗا وَحِينَ تُظۡهِرُونَ ﴿١٨﴾ يُخۡرِجُ ٱلۡحَيَّ مِنَ ٱلۡمَيِّتِ وَيُخۡرِجُ
ٱلۡمَيِّتَ مِنَ ٱلۡحَيِّ وَيُحۡيِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَاۚ وَكَذَٰلِكَ تُخۡرَجُونَ
﴿١٩﴾ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنۡ خَلَقَكُم مِّن تُرَابٖ ثُمَّ إِذَآ أَنتُم بَشَرٞ
تَنتَشِرُونَ ﴿٢٠﴾ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنۡ خَلَقَ لَكُم مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ
أَزۡوَٰجٗا لِّتَسۡكُنُوٓاْ إِلَيۡهَا وَجَعَلَ بَيۡنَكُم مَّوَدَّةٗ وَرَحۡمَةً
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَتَفَكَّرُونَ ﴿٢١﴾ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ
خَلۡقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَٱخۡتِلَٰفُ أَلۡسِنَتِكُمۡ وَأَلۡوَٰنِكُمۡۚ
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّلۡعَٰلِمِينَ ﴿٢٢﴾ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ مَنَامُكُم
بِٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِ وَٱبۡتِغَآؤُكُم مِّن فَضۡلِهِۦٓۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَسۡمَعُونَ ﴿٢٣﴾ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ يُرِيكُمُ ٱلۡبَرۡقَ
خَوۡفٗا وَطَمَعٗا وَيُنَزِّلُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَيُحۡيِۦ بِهِ ٱلۡأَرۡضَ
بَعۡدَ مَوۡتِهَآۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ ﴿٢٤﴾

(16) Amma kuma waɗanda suka kafirta suka kuma ƙaryata ayoyinmu da haɗuwa da ranar lahira, to waɗannan za a halartar da su cikin azaba
(17) To tsarki ya tabbata ga Allah yayin kuka shiga lokacin maraice, da kuma yayin da kuka wayi gari
(18) Yabo kuma nasa ne a cikin sammai da ƙasa, da kuma yayin da kuka yi yammaci da kuma shigowarku lokacin azahar
(19) Yana fitar da rayayye daga matacce, Yana kuma fitar da matacce daga rayayye, kuma Yana raya ƙasa bayan mutuwarta. Kamar haka ne kuma za a fito da ku (daga ƙaburburanku)
(20) Yana daga ayoyinsa cewa Ya halicce ku daga turɓaya, sannan kuma sai ga ku mutane kun warwatsu (a ko'ina)
(21) Yana kuma daga ayoyinsa cewa Ya halitta muku mata daga jinsinku don ku samu nutsuwa gare su, Ya kuma sanya soyayya da jin ƙai tsakaninku. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutane masu tunani
(22) Yana kuma daga cikin ayoyinsa halittar sammai da ƙasa da kuma sassaɓawar harsunanku da launukanku. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga ma'abota ilimi
(23) Yana kuma daga cikin ayoyinsa barcinku da daddare da kuma rana da neman falalarsa da kuke yi. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga masu ji (na lura)
(24) Yana kuma daga cikin ayoyinsa nuna muku walƙiya da Yake yi don tsoratarwa da kwaɗaitarwa, Ya kuma saukar da ruwa daga sama, sai Ya raya ƙasa da shi bayan mutuwarta. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutane da suke hankalta

وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَن تَقُومَ ٱلسَّمَآءُ وَٱلْأَرْضُ بِأَمْرِهِۦ ۚ ثُمَّ إِذَا دَعَاكُمْ
دَعْوَةً مِّنَ ٱلْأَرْضِ إِذَآ أَنتُمْ تَخْرُجُونَ ﴿٢٥﴾ وَلَهُۥ مَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ ۖ كُلٌّ لَّهُۥ قَٰنِتُونَ ﴿٢٦﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى يَبْدَؤُا۟ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ
يُعِيدُهُۥ وَهُوَ أَهْوَنُ عَلَيْهِ ۚ وَلَهُ ٱلْمَثَلُ ٱلْأَعْلَىٰ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٢٧﴾ ضَرَبَ لَكُم مَّثَلًا
مِّنْ أَنفُسِكُمْ ۖ هَل لَّكُم مِّن مَّا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُم مِّن
شُرَكَآءَ فِى مَا رَزَقْنَٰكُمْ فَأَنتُمْ فِيهِ سَوَآءٌ تَخَافُونَهُمْ
كَخِيفَتِكُمْ أَنفُسَكُمْ ۚ كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ
يَعْقِلُونَ ﴿٢٨﴾ بَلِ ٱتَّبَعَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓا۟ أَهْوَآءَهُم بِغَيْرِ عِلْمٍ ۖ
فَمَن يَهْدِى مَنْ أَضَلَّ ٱللَّهُ ۖ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿٢٩﴾ فَأَقِمْ
وَجْهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفًا ۚ فِطْرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِى فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيْهَا ۚ
لَا تَبْدِيلَ لِخَلْقِ ٱللَّهِ ۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلْقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ
ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٣٠﴾ * مُنِيبِينَ إِلَيْهِ وَٱتَّقُوهُ وَأَقِيمُوا۟
ٱلصَّلَوٰةَ وَلَا تَكُونُوا۟ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٣١﴾ مِنَ ٱلَّذِينَ فَرَّقُوا۟
دِينَهُمْ وَكَانُوا۟ شِيَعًا ۖ كُلُّ حِزْبٍۭ بِمَا لَدَيْهِمْ فَرِحُونَ ﴿٣٢﴾

(25) Yana kuma daga cikin ayoyinsa sama da ƙasa su tsaya da umarninsa. Sannan kuma yayin da Ya kira ku (don ku tashi) daga ƙasa sai ga ku kuna fitowa

(26) Kuma duk waɗanda suke cikin sammai da ƙasa nasa ne; dukkaninsu masu biyayya ne gare Shi

(27) Shi ne wanda Yake farar halittu, sannan Ya dawo da su (bayan mutuwa. Yin haka) kuwa shi ya fi sauƙi a gare Shi. Kuma siffofi mafiya ɗaukaka sun tabbata gare Shi a cikin sammai da ƙasa, kuma Shi ne Mabuwayi, Mai hikima

(28) Ya ba ku misali daga kawunanku; shin kuna da wasu abokan tarayya daga bayinku da kuka mallaka a kan abin da Muka arzuta ku (da shi), ku da su ku zama daidai kuke game da wannan; kuna ma jin tsoron su kamar yanda kuke tsoron junanku? Kamar haka Muke rarrabe ayoyin (filla-filla) ga mutanen da suke hankalta

(29) Ba haka ba ne, waɗanda suka yi zalunci dai sun bi son ransu ne ba tare da wani ilimi ba; to wane ne zai shiryar da wanda Allah Ya ɓatar? Kuma ba su da wasu mataimaka

(30) To sai ka tsayar da fuskarka ga addini mai kauce wa ɓarna. (Shi ne) asalin halittar da Allah Ya halicci mutane a kanta[1]. Ba wani canji ga halittar Allah. Wannan shi ne miƙaƙƙen addini, sai dai kuma yawancin mutane ba su san (haka ba)

(31) (Kuma) kuna masu komawa zuwa gare Shi (wato Allah) kuma ku kiyaye dokokinsa ku kuma tsai da salla kuma kada ku zamanto cikin mushirikai

(32) Irin waɗanda suka rarraba addininsu suka kuma zamanto ƙungiya-ƙungiya; kowacce ƙungiya tana mai farin ciki da abin da yake nata

(1) Watau kaxaita Allah da bauta. Addinin Musulunci shi ne addinin da ya dace da halittar xan'adam ta asali, watau fixra.

وَإِذَا مَسَّ ٱلنَّاسَ ضُرٌّ دَعَوْا۟ رَبَّهُم مُّنِيبِينَ إِلَيْهِ ثُمَّ إِذَآ أَذَاقَهُم
مِّنْهُ رَحْمَةً إِذَا فَرِيقٌ مِّنْهُم بِرَبِّهِمْ يُشْرِكُونَ ﴿٣٣﴾ لِيَكْفُرُوا۟ بِمَآ
ءَاتَيْنَٰهُمْ ۚ فَتَمَتَّعُوا۟ فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿٣٤﴾ أَمْ أَنزَلْنَا عَلَيْهِمْ
سُلْطَٰنًا فَهُوَ يَتَكَلَّمُ بِمَا كَانُوا۟ بِهِۦ يُشْرِكُونَ ﴿٣٥﴾ وَإِذَآ أَذَقْنَا
ٱلنَّاسَ رَحْمَةً فَرِحُوا۟ بِهَا ۖ وَإِن تُصِبْهُمْ سَيِّئَةٌۢ بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ
إِذَا هُمْ يَقْنَطُونَ ﴿٣٦﴾ أَوَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّ ٱللَّهَ يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ
وَيَقْدِرُ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٣٧﴾ فَـَٔاتِ ذَا ٱلْقُرْبَىٰ
حَقَّهُۥ وَٱلْمِسْكِينَ وَٱبْنَ ٱلسَّبِيلِ ۚ ذَٰلِكَ خَيْرٌ لِّلَّذِينَ يُرِيدُونَ
وَجْهَ ٱللَّهِ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ﴿٣٨﴾ وَمَآ ءَاتَيْتُم مِّن رِّبًا
لِّيَرْبُوَا۟ فِىٓ أَمْوَٰلِ ٱلنَّاسِ فَلَا يَرْبُوا۟ عِندَ ٱللَّهِ ۖ وَمَآ ءَاتَيْتُم مِّن
زَكَوٰةٍ تُرِيدُونَ وَجْهَ ٱللَّهِ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُضْعِفُونَ ﴿٣٩﴾
ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَكُمْ ثُمَّ رَزَقَكُمْ ثُمَّ يُمِيتُكُمْ ثُمَّ يُحْيِيكُمْ ۖ هَلْ مِن
شُرَكَآئِكُم مَّن يَفْعَلُ مِن ذَٰلِكُم مِّن شَىْءٍ ۚ سُبْحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ
عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٤٠﴾ ظَهَرَ ٱلْفَسَادُ فِى ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ بِمَا كَسَبَتْ
أَيْدِى ٱلنَّاسِ لِيُذِيقَهُم بَعْضَ ٱلَّذِى عَمِلُوا۟ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿٤١﴾

(33) Idan kuma wani matsi ya sami mutane sai su roƙi Ubangijinsu suna masu komawa gare Shi, sannan kuma idan Ya ɗanɗana musu rahama daga gare Shi sai ka ga wata ƙungiyar daga cikinsu suna tarayya da Ubangijinsu
(34) Don su kafirce wa abin da Muka ba su. To ku ji dadi, da sannu za ku sani
(35) Ko kuma Mun saukar musu da wani littafi ne wanda shi ne yake magana da abin da suka kasance suna shirka da shi?
(36) Idan kuma Muka ɗanɗana wa mutane rahama sai su yi farin ciki da ita; idan kuwa wata masifa ta same su saboda abin da hannayensu suka gabatar sai ka gan su suna ɗebe ƙauna
(37) nzu ba su gani ba cewa Allah Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, Yana kuma ƙuntatawa (ga wanda ya ga dama)? Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutanen da suke yin imani
(38) Sannan ka bai wa (ɗan'uwa) makusanci haƙƙinsa da miskini da matafiyi. Wannan shi ya fi alheri ga waɗanda suke nufin Fuskar Allah; kuma waɗannan su ne masu rabauta
(39) Kuma abin da kuka bayar na riba don ya ƙaru a cikin dukiyoyin mutane, to ba ya ƙaruwa a wurin Allah(1); abin kuma da kuka bayar na zakka kuna masu nufin Fuskar Allah, to waɗannan su ne masu ninninka (ladansu)
(40) Allah (Shi ne) Wanda Ya halicce ku sannan Ya arzuta ku sannan Shi zai kashe ku sannan Ya raya ku; shin a cikin abokan tarayyarku akwai wanda zai aikata wani abu daga wannan? Tsarki ya tabbata a gare Shi, Ya kuma ɗaukaka daga abin da suke tarawa (da Shi).
(41) Ɓarna ta bayyana a kan tudu da kuma (cikin) ruwa saboda abubuwan da hannayen mutane suka aikata don a ɗanɗana musu sashin abin da suka aikata, ko watakila sa juyo

(1) Da yawa daga cikin malamai sun fassara wannan gavar da cewa, ana nufin wanda zai bayar da kyauta yana nufin a mayar masa da fiye da abin da ya bayar, to ba shi da lada a wurin Allah.

قُلْ سِيرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ فَٱنظُرُوا۟ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلُ ۚ
كَانَ أَكْثَرُهُم مُّشْرِكِينَ ﴿٤٢﴾ فَأَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ ٱلْقَيِّمِ مِن
قَبْلِ أَن يَأْتِىَ يَوْمٌ لَّا مَرَدَّ لَهُۥ مِنَ ٱللَّهِ ۖ يَوْمَئِذٍ يَصَّدَّعُونَ ﴿٤٣﴾ مَن
كَفَرَ فَعَلَيْهِ كُفْرُهُۥ ۖ وَمَنْ عَمِلَ صَٰلِحًا فَلِأَنفُسِهِمْ يَمْهَدُونَ ﴿٤٤﴾
لِيَجْزِىَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِن فَضْلِهِۦٓ ۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ
ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٤٥﴾ وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَن يُرْسِلَ ٱلرِّيَاحَ مُبَشِّرَٰتٍ وَلِيُذِيقَكُم
مِّن رَّحْمَتِهِۦ وَلِتَجْرِىَ ٱلْفُلْكُ بِأَمْرِهِۦ وَلِتَبْتَغُوا۟ مِن فَضْلِهِۦ وَلَعَلَّكُمْ
تَشْكُرُونَ ﴿٤٦﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ رُسُلًا إِلَىٰ قَوْمِهِمْ فَجَآءُوهُم
بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَٱنتَقَمْنَا مِنَ ٱلَّذِينَ أَجْرَمُوا۟ ۖ وَكَانَ حَقًّا عَلَيْنَا نَصْرُ
ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٤٧﴾ ٱللَّهُ ٱلَّذِى يُرْسِلُ ٱلرِّيَاحَ فَتُثِيرُ سَحَابًا فَيَبْسُطُهُۥ
فِى ٱلسَّمَآءِ كَيْفَ يَشَآءُ وَيَجْعَلُهُۥ كِسَفًا فَتَرَى ٱلْوَدْقَ يَخْرُجُ مِنْ
خِلَٰلِهِۦ ۖ فَإِذَآ أَصَابَ بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦٓ إِذَا هُمْ يَسْتَبْشِرُونَ
﴿٤٨﴾ وَإِن كَانُوا۟ مِن قَبْلِ أَن يُنَزَّلَ عَلَيْهِم مِّن قَبْلِهِۦ لَمُبْلِسِينَ
﴿٤٩﴾ فَٱنظُرْ إِلَىٰٓ ءَاثَٰرِ رَحْمَتِ ٱللَّهِ كَيْفَ يُحْىِ ٱلْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَآ ۚ
إِنَّ ذَٰلِكَ لَمُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰ ۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٥٠﴾

(42) Ka ce (da su): “Ku yi tafiya mana a bayan ƙasa sannan ku duba ku ga yadda ƙarshen waɗanda suke gabaninku ya zama. Yawancinsu sun kasance mushirikai

(43) To sai ka tsai da fuskarka ga addini madaidaici tun kafin ranar nan da ba ta da makawa ta zo daga Allah; a wannan ranar ne (mutane) za su rarraba[1]

(44) Wanda ya kafirta to zunubin kafircinsa yana kansa; waɗanda kuwa suka yi aiki kyakkyawa, to kansu suke yi wa shimfiɗa (ta alheri)

(45) Don (Allah) Ya saka wa waɗanda suka yi imani suka yi ayyuka nagari daga falalarsa. Lalle Shi (Allah) ba Ya son kafirai

(46) Yana kuma daga ayoyinsa cewa Yana aiko iska tana mai yin albishir (da ruwa) kuma don Ya ɗanɗana muku rahamarsa, don kuma jiragen ruwa su riƙa gudana da umarninsa, kuma don ku nema daga falalarsa ko kwa gode

(47) Haƙiƙa kuma Mun aiko wasu manzanni gabaninka zuwa ga mutanensu, sai suka zo musu da hujjoji bayyanannu, sai Muka azabtar da waɗanda suka kafirce, kuma taimakon muminai ya zama haƙƙi ne a kanmu

(48) Allah (Shi ne) wanda Yake aiko da iska sai ta motsa girgije, sai Ya shimfiɗa shi a (sararin) sama yadda Ya ga dama, Ya kuma sanya shi yanki-yanki, sai ka ga ruwa yana fitowa ta tsakaninsa, to idan Ya saukar da shi ga waɗanda Ya ga dama daga bayinsa sai ka gan su suna ta murna

(49) Ko da yake da can kafin a saukar musu shi tabbas sun kasance masu ɗebe ƙauna

(50) To sai ka yi duba ga guraben rahamar Allah (ka ga) yadda Yake raya ƙasa bayan mutuwarta. Lalle wannan tabbas Mai raya matattu ne, kuma Mai iko ne a kan komai

(1) Watau wasu su tafi gidan Aljanna, wasu kuma su nufi wutar jahannama.

وَلَئِنْ أَرْسَلْنَا رِيحًا فَرَأَوْهُ مُصْفَرًّا لَّظَلُّوا مِنۢ بَعْدِهِۦ يَكْفُرُونَ
﴿٥١﴾ فَإِنَّكَ لَا تُسْمِعُ ٱلْمَوْتَىٰ وَلَا تُسْمِعُ ٱلصُّمَّ ٱلدُّعَآءَ إِذَا وَلَّوْا
مُدْبِرِينَ ﴿٥٢﴾ وَمَآ أَنتَ بِهَٰدِ ٱلْعُمْىِ عَن ضَلَٰلَتِهِمْ ۖ إِن تُسْمِعُ إِلَّا
مَن يُؤْمِنُ بِـَٔايَٰتِنَا فَهُم مُّسْلِمُونَ ﴿٥٣﴾ ۞ ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَكُم
مِّن ضَعْفٍ ثُمَّ جَعَلَ مِنۢ بَعْدِ ضَعْفٍ قُوَّةً ثُمَّ جَعَلَ مِنۢ بَعْدِ
قُوَّةٍ ضَعْفًا وَشَيْبَةً ۚ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ ۚ وَهُوَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْقَدِيرُ
﴿٥٤﴾ وَيَوْمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يُقْسِمُ ٱلْمُجْرِمُونَ مَا لَبِثُوا۟ غَيْرَ
سَاعَةٍ ۚ كَذَٰلِكَ كَانُوا۟ يُؤْفَكُونَ ﴿٥٥﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟
ٱلْعِلْمَ وَٱلْإِيمَٰنَ لَقَدْ لَبِثْتُمْ فِى كِتَٰبِ ٱللَّهِ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْبَعْثِ ۖ
فَهَٰذَا يَوْمُ ٱلْبَعْثِ وَلَٰكِنَّكُمْ كُنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿٥٦﴾ فَيَوْمَئِذٍ
لَّا يَنفَعُ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ مَعْذِرَتُهُمْ وَلَا هُمْ يُسْتَعْتَبُونَ
﴿٥٧﴾ وَلَقَدْ ضَرَبْنَا لِلنَّاسِ فِى هَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ مِن كُلِّ مَثَلٍ ۚ
وَلَئِن جِئْتَهُم بِـَٔايَةٍ لَّيَقُولَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ إِنْ أَنتُمْ إِلَّا
مُبْطِلُونَ ﴿٥٨﴾ كَذَٰلِكَ يَطْبَعُ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِ ٱلَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ
﴿٥٩﴾ فَٱصْبِرْ ۖ إِنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ ۖ وَلَا يَسْتَخِفَّنَّكَ ٱلَّذِينَ لَا يُوقِنُونَ ﴿٦٠﴾

(51) Tabbas kuma in da za Mu aiko da iska su gan shi (wato amfanin gonarsu) ya yi fatsi-fatsi da sai sun ci gaba da kafirce wa (Allah) bayan haka
(52) To lalle kai ba ka iya jiyar da matattu, kuma ba ka iya jiyar da kurame kira lokacin da suka juya suna masu ba da baya
(53) Kuma kai ba mai iya shiryar da makafi (wato ɓatattu) ba ne daga ɓatansu; ba wadanda kake iya jiyarwa sai wadanda suka yi imani da ayoyinmu don haka suna masu mika wuya
(54) Allah (Shi ne) Wanda Ya halicce ku daga rauni, sannan kuma Ya sanya ƙarfi bayan raunin, sannan kuma Ya sanya rauni da furfura bayan ƙarfi. Yana halittar abin da Ya ga dama; Shi ne kuwa Masani, Mai iko
(55) Kuma a ranar da alƙiyama za ta tashi masu manyan laifuka za su rantse (kan) ba su zauna ba (a ƙaburburansu) fiye da sa'a ɗaya. Kamar haka suka kasance ana karkatar da su (daga gaskiya)
(56) Wadanda kuwa aka bai wa ilimi da imani sai suka ce: "Haƙiƙa kun zauna ne gwargwadon yadda Allah Ya rubuta muku a littafinsa har zuwa ranar tashi; to wannan kuma ita ce ranar tashin, sai dai kuma ku kun kasance ba ku san (haka) ba."
(57) To a wannan ranar wadanda suka yi zalunci hanzarinsu ba zai amfane su ba, kuma ba za a nemi su kawo wani uzuri ba
(58) Kuma haƙiƙa Mun ba wa mutane kowane irin misali a cikin wannan Alƙur'anin. Kuma tabbas idan da za ka zo musu da wata aya lallai da wadanda suka kafirce sun ce: "Ai ku maɓarnata ne kawai."
(59) Kamar haka ne Allah Yake toshe zukatan wadanda ba sa sanin (gaskiya)
(60) Sai ka yi haƙuri, lalle alƙawarin Allah gaskiya ne; kada kuma wadanda ba sa sakankancewa (da alƙiyama) su ingiza ka (har ka kasa haƙuri)

Sura Lukman

سُورَةُ لُقْمَانَ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

الٓمٓ ﴿١﴾ تِلْكَ ءَايَٰتُ ٱلْكِتَٰبِ ٱلْحَكِيمِ ﴿٢﴾ هُدًى وَرَحْمَةً
لِّلْمُحْسِنِينَ ﴿٣﴾ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤْتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُم
بِٱلْءَاخِرَةِ هُمْ يُوقِنُونَ ﴿٤﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ عَلَىٰ هُدًى مِّن رَّبِّهِمْ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ
هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ﴿٥﴾ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَشْتَرِى لَهْوَ ٱلْحَدِيثِ
لِيُضِلَّ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ بِغَيْرِ عِلْمٍ وَيَتَّخِذَهَا هُزُوًا ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ
عَذَابٌ مُّهِينٌ ﴿٦﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِ ءَايَٰتُنَا وَلَّىٰ مُسْتَكْبِرًا
كَأَن لَّمْ يَسْمَعْهَا كَأَنَّ فِىٓ أُذُنَيْهِ وَقْرًا ۖ فَبَشِّرْهُ بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿٧﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمْ جَنَّٰتُ ٱلنَّعِيمِ ﴿٨﴾
خَٰلِدِينَ فِيهَا ۖ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقًّا ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٩﴾ خَلَقَ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ بِغَيْرِ عَمَدٍ تَرَوْنَهَا ۖ وَأَلْقَىٰ فِى ٱلْأَرْضِ رَوَٰسِىَ أَن تَمِيدَ
بِكُمْ وَبَثَّ فِيهَا مِن كُلِّ دَآبَّةٍ ۚ وَأَنزَلْنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَنۢبَتْنَا
فِيهَا مِن كُلِّ زَوْجٍ كَرِيمٍ ﴿١٠﴾ هَٰذَا خَلْقُ ٱللَّهِ فَأَرُونِى مَاذَا
خَلَقَ ٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦ ۚ بَلِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿١١﴾

(1) ALIF LAM MIM[1] .
(2) Waɗannan ayoyin littafi ne mai hikima
(3) Shiriya ne da rahama ga masu kyautatawa
(4) Waɗanda suke tsai da salla suke kuma ba da zakka alhali su kuma suna masu sakankancewa da ranar lahira
(5) Waɗannan suna kan shiriya daga Ubangijinsu; waɗannan su ne masu rabauta
(6) Daga mutane kuma akwai wanda yake sayen zantuka na sharholiya[2] don ya ɓatar (da mutane) daga hanyar Allah ba tare da wani ilimi ba, yana kuma rikon ta abar yi wa izgili. (Irin) waɗannan azaba mai wulakantarwa ta tabbata gare su
(7) Idan kuma ana karanta masa ayoyinmu sai ya juya yana mai girman kai kamar bai ji su ba, kamar a ce akwai wani nauyi a cikin kunnuwansa; to ka yi masa albishir da azaba mai raɗaɗi
(8) Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari suna da (sakamakon) gidajen Aljanna na ni'ima
(9) Suna madawwama a cikinsu; alkawarin Allah kuwa gaskiya ne. Kuma Shi Mabuwayi ne, Mai hikima
(10) Ya halicci sammai ba tare da wani ginshiki da kuke ganin sa ba, Ya kuma kafa manya-manyan duwatsu a cikin ƙasa don kada ta rika tangal-tangal da ku, Ya kuma yaɗa kowace irin dabba a cikinta. Kuma Mun saukar da ruwa daga sama sai Muka tsirar da kowane irin dangin tsiro mai ƙayatarwa
(11) Wannan (ita ce) halittar Allah, sai ku nuna min abin da waɗanda ba Shi ba suka halitta. A'a, su dai azzalumai suna cikin ɓata ne mabayyani

(1) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8..

(2) Watau kamar waqoqin banza da kaxa-kaxe da labaru marasa manufa, don ya shagaltar da mutane daga sauraren Alqur'ani, ya vatar da su daga addinin Allah.

وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا لُقْمَٰنَ ٱلْحِكْمَةَ أَنِ ٱشْكُرْ لِلَّهِ ۚ وَمَن يَشْكُرْ فَإِنَّمَا
يَشْكُرُ لِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَنِىٌّ حَمِيدٌ ﴿١٢﴾ وَإِذْ قَالَ
لُقْمَٰنُ لِٱبْنِهِۦ وَهُوَ يَعِظُهُۥ يَٰبُنَىَّ لَا تُشْرِكْ بِٱللَّهِ ۖ إِنَّ ٱلشِّرْكَ
لَظُلْمٌ عَظِيمٌ ﴿١٣﴾ وَوَصَّيْنَا ٱلْإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيْهِ حَمَلَتْهُ أُمُّهُۥ
وَهْنًا عَلَىٰ وَهْنٍ وَفِصَٰلُهُۥ فِى عَامَيْنِ أَنِ ٱشْكُرْ لِى وَلِوَٰلِدَيْكَ
إِلَىَّ ٱلْمَصِيرُ ﴿١٤﴾ وَإِن جَٰهَدَاكَ عَلَىٰٓ أَن تُشْرِكَ بِى مَا لَيْسَ
لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ فَلَا تُطِعْهُمَا ۖ وَصَاحِبْهُمَا فِى ٱلدُّنْيَا مَعْرُوفًا ۖ
وَٱتَّبِعْ سَبِيلَ مَنْ أَنَابَ إِلَىَّ ۚ ثُمَّ إِلَىَّ مَرْجِعُكُمْ فَأُنَبِّئُكُم
بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿١٥﴾ يَٰبُنَىَّ إِنَّهَآ إِن تَكُ مِثْقَالَ حَبَّةٍ مِّنْ
خَرْدَلٍ فَتَكُن فِى صَخْرَةٍ أَوْ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ أَوْ فِى ٱلْأَرْضِ يَأْتِ
بِهَا ٱللَّهُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَطِيفٌ خَبِيرٌ ﴿١٦﴾ يَٰبُنَىَّ أَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ وَأْمُرْ
بِٱلْمَعْرُوفِ وَٱنْهَ عَنِ ٱلْمُنكَرِ وَٱصْبِرْ عَلَىٰ مَآ أَصَابَكَ ۖ إِنَّ ذَٰلِكَ
مِنْ عَزْمِ ٱلْأُمُورِ ﴿١٧﴾ وَلَا تُصَعِّرْ خَدَّكَ لِلنَّاسِ وَلَا تَمْشِ فِى ٱلْأَرْضِ
مَرَحًا ۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخْتَالٍ فَخُورٍ ﴿١٨﴾ وَٱقْصِدْ فِى مَشْيِكَ
وَٱغْضُضْ مِن صَوْتِكَ ۚ إِنَّ أَنكَرَ ٱلْأَصْوَٰتِ لَصَوْتُ ٱلْحَمِيرِ ﴿١٩﴾

(12) Hakika kuma Mun bai wa Lukumanu[1] hikima cewa: "Ka yi godiya ga Allah. Kuma duk wanda yake godewa to yana godewa ne don kansa, wanda kuwa ya kafirta to lalle Allah Mawadaci ne, Sha-yabo."

(13) Kuma (ka tuna) lokacin da Lukumanu ya ce da ɗansa a yayin da yake yi masa wa'azi: "Ya kai ɗanɗana, kada ka yi shirka da Allah; lalle ita shirka zalunci ne mai girma

(14) Kuma Mun yi wa mutum wasiyya game da iyayensa, mahaifiyarsa ta ɗauke shi a cikinta rauni a kan rauni, yaye shi kuwa a cikin shekara biyu ne, saboda haka ka gode min da kuma iyayenka, makoma gare Ni take

(15) Idan kuma suka matsa maka kan ka yi tarayya da Ni game da abin da ba ka da wani sani a kansa, to kada ka bi su; kuma ka yi zaman duniya da su ta kyakkyawar hanya; ka kuma bi hanyar wanda ya mayar da al'amarinsa gare Ni. Sannan kuma zuwa gare Ni ne kawai makomarku, sai in ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa

(16) (Lukumanu ya ci gaba da cewa): "Ya kai ɗanɗana, lalle ita (kyakkyawa ko mummuna) in ta kasance daidai da ƙwayar komayya, sannan kuma ta zamanto cikin ƙaton dutse ko kuma cikin sammai ko cikin ƙasa, to Allah zai zo da ita. Lalle Allah Mai tausasawa ne, Masanin (komai)

(17) "Ya kai ɗanɗana, ka tsayar da salla kuma ka yi umarni da aikata alheri, ka kuma hana aikata mummunan aiki, kuma ka yi haƙuri bisa duk abin da ya same ka; lalle wannan yana daga manyan al'amura

(18) "Kada kuma ka riƙa ɗauke wa mutane fuskarka[2], kuma kada ka yi tafiya a ban ƙasa kana mai taƙama. Lalle Allah ba Ya son duk wani mai taƙama, mai fariya

(19) "Kuma ka tsakaita tafiyarka, kuma ka yi ƙasa-ƙasa da muryarka. Lalle mafi munin muryoyi ita ce muryar jakai."

(1) Wani salihin bawa ne da Allah ya hore masa hikima da ilimi. Wasu masana tarihi sun ce yarayu ne a zamanin Annabi Dawud ( ).

(2) Watau yana umartar sa da ya zama mai sakin fuska da haba-haba da jama'a.

أَلَمْ تَرَوْا۟ أَنَّ ٱللَّهَ سَخَّرَ لَكُم مَّا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ وَأَسْبَغَ
عَلَيْكُمْ نِعَمَهُۥ ظَٰهِرَةً وَبَاطِنَةً ۗ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يُجَٰدِلُ فِى ٱللَّهِ
بِغَيْرِ عِلْمٍ وَلَا هُدًى وَلَا كِتَٰبٍ مُّنِيرٍ ﴿٢٠﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱتَّبِعُوا۟
مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ قَالُوا۟ بَلْ نَتَّبِعُ مَا وَجَدْنَا عَلَيْهِ ءَابَآءَنَآ ۗ أَوَلَوْ كَانَ
ٱلشَّيْطَٰنُ يَدْعُوهُمْ إِلَىٰ عَذَابِ ٱلسَّعِيرِ ﴿٢١﴾ ۞ وَمَن يُسْلِمْ
وَجْهَهُۥٓ إِلَى ٱللَّهِ وَهُوَ مُحْسِنٌ فَقَدِ ٱسْتَمْسَكَ بِٱلْعُرْوَةِ ٱلْوُثْقَىٰ ۗ
وَإِلَى ٱللَّهِ عَٰقِبَةُ ٱلْأُمُورِ ﴿٢٢﴾ وَمَن كَفَرَ فَلَا يَحْزُنكَ كُفْرُهُۥٓ ۚ
إِلَيْنَا مَرْجِعُهُمْ فَنُنَبِّئُهُم بِمَا عَمِلُوٓا۟ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ
﴿٢٣﴾ نُمَتِّعُهُمْ قَلِيلًا ثُمَّ نَضْطَرُّهُمْ إِلَىٰ عَذَابٍ غَلِيظٍ ﴿٢٤﴾
وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ۚ قُلِ
ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ۚ بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٢٥﴾ لِلَّهِ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْغَنِىُّ ٱلْحَمِيدُ ﴿٢٦﴾ وَلَوْ أَنَّمَا فِى ٱلْأَرْضِ
مِن شَجَرَةٍ أَقْلَٰمٌ وَٱلْبَحْرُ يَمُدُّهُۥ مِنۢ بَعْدِهِۦ سَبْعَةُ أَبْحُرٍ
مَّا نَفِدَتْ كَلِمَٰتُ ٱللَّهِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٢٧﴾ مَّا خَلْقُكُمْ
وَلَا بَعْثُكُمْ إِلَّا كَنَفْسٍ وَٰحِدَةٍ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌۢ بَصِيرٌ ﴿٢٨﴾

(20) Yanzu ba kwa gani cewa Allah Ya hore muku abin da yake cikin sammai da kuma abin da yake cikin ƙasa, Ya kuma cika muku ni'imominsa na sarari da na ɓoye? Daga mutane kuma akwai waɗanda suke jayayya game da Allah ba tare da wani ilimi ko wata shiriya ba, ba kuma tare da wani littafi mai haskakawa ba
(21) Idan kuma aka ce da su: "Ku bi abin da Allah Ya saukar", sai su ce: "A'a, mu muna bin abin da muka sami iyayenmu ne a kansa." Yanzu (sa yi haka) ko da Shaiɗan ya zamanto yana kiran su zuwa ga azaba ta (wuta) mai ruruwa?
(22) Wanda kuma ya miƙa kansa ga Allah, yana kuma mai kyautatawa[1], to haƙiƙa ya yi riƙo da igiya ƙwaƙƙwara. Kuma ƙarshen al'amura zuwa ga Allah ne
(23) Duk kuwa wanda ya kafirta, to kada kafircinsa ya ɓata maka rai. Zuwa gare Mu ne kawai makomarsu take, sai Mu ba su labarin abin da suka aikata. Lalle Allah Masanin abin da yake cikin ƙiraza ne
(24) Za Mu jiyar da su daɗi ɗan kaɗan sannan Mu tilasta su zuwa ga azaba mai kauri
(25) Tabbas kuma in ka tambaye su: "Wane ne ya halicci sammai da ƙasa?" Tabbas za su ce: "Allah ne." To ka ce: "Alhamdu lillahi." A'a, yawancinsu dai ba sa sanin (haka)
(26) Abin da yake cikin sammai da ƙasa na Allah ne. Lalle Allah Shi ne Mawadaci, Sha-yabo
(27) Idan kuwa da a ce, duk bishiyar da take bayan ƙasa alƙaluma ne, kogi kuma (ya zama tawadarsu), bayansa kuma akwai wasu kogunan guda bakwai ƙari a kansa to kalmomin Allah ba za su ƙare ba. Lalle Allah Mabuwayi ne, Mai hikima
(28) Halittarku da tayar da ku bai wuce tamkar na rai ɗaya ba. Lalle

(1) Watau ya kaxaita Allah da bauta, ya kuma kyautata aikinsa.

أَلَمْ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ يُولِجُ ٱلَّيْلَ فِى ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِى ٱلَّيْلِ
وَسَخَّرَ ٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ كُلٌّ يَجْرِىٓ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى وَأَنَّ ٱللَّهَ
بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ﴿٢٩﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْحَقُّ وَأَنَّ مَا يَدْعُونَ
مِن دُونِهِ ٱلْبَٰطِلُ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْعَلِىُّ ٱلْكَبِيرُ ﴿٣٠﴾ أَلَمْ تَرَ أَنَّ
ٱلْفُلْكَ تَجْرِى فِى ٱلْبَحْرِ بِنِعْمَتِ ٱللَّهِ لِيُرِيَكُم مِّنْ ءَايَٰتِهِۦٓ ۚ إِنَّ
فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّكُلِّ صَبَّارٍ شَكُورٍ ﴿٣١﴾ وَإِذَا غَشِيَهُم مَّوْجٌ
كَٱلظُّلَلِ دَعَوُا۟ ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ فَلَمَّا نَجَّىٰهُمْ إِلَى ٱلْبَرِّ
فَمِنْهُم مُّقْتَصِدٌ ۚ وَمَا يَجْحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَّا كُلُّ خَتَّارٍ كَفُورٍ
﴿٣٢﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱتَّقُوا۟ رَبَّكُمْ وَٱخْشَوْا۟ يَوْمًا لَّا يَجْزِى وَالِدٌ
عَن وَلَدِهِۦ وَلَا مَوْلُودٌ هُوَ جَازٍ عَن وَالِدِهِۦ شَيْـًٔا ۚ إِنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ
حَقٌّ ۖ فَلَا تَغُرَّنَّكُمُ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا وَلَا يَغُرَّنَّكُم بِٱللَّهِ
ٱلْغَرُورُ ﴿٣٣﴾ إِنَّ ٱللَّهَ عِندَهُۥ عِلْمُ ٱلسَّاعَةِ وَيُنَزِّلُ ٱلْغَيْثَ
وَيَعْلَمُ مَا فِى ٱلْأَرْحَامِ ۖ وَمَا تَدْرِى نَفْسٌ مَّاذَا تَكْسِبُ غَدًا ۖ
وَمَا تَدْرِى نَفْسٌۢ بِأَىِّ أَرْضٍ تَمُوتُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ خَبِيرٌ ﴿٣٤﴾

سُورَةُ السَّجْدَةِ

(29) Yanzu ba ka gani cewa Allah Yana shigar da dare cikin rana, Yana kuma shigar da rana cikin dare, Ya kuma hore (muku) rana da wata, kowannensu yana tafiya zuwa ga lokaci iyakantacce, kuma lalle Allah Masanin abin da kuke aikatawa ne?

(30) Wannan kuwa (suna samuwa ne) saboda Allah Shi ne Gaskiya, lalle kuma abin da suke bauta wa ba Shi ba ƙarya ne, lalle kuma Shi Allah Maɗaukaki ne, Mai girma

(31) Ba ka gani cewa jiragen ruwa suna tafiya a cikin kogi da ni'imar Allah, don Ya nuna muku (wasu) daga ayoyinsa? Lalle a game da wannan akwai ayoyi ga duk mai yawan haƙuri, mai yawan godiya

(32) Idan kuwa wata igiyar ruwa kamar duwatsu ta kere su, sai su roƙi Allah suna tsantsanta addini a gare Shi, to kuma idan Ya tserar da su zuwa gaci, to akan sami tsaka-tsaki daga cikinsu. Kuma babu mai yin jayayya da ayoyinmu sai duk wani mayaudari, mai butulci

(33) Ya ku mutane, ku kiyaye dokokin Ubangijinku, kuma ku ji tsoron ranar da mahaifi ba zai amfana wa ɗansa komai ba, kuma ɗan shi ma ba zai amfana wa mahaifinsa komai ba. Lalle alƙawarin Allah gaskiya ne; to kada rayuwar duniya ta ruɗe ku, kuma (Shaiɗan) mai ruɗarwa kada ya ruɗe ku game da Allah

(34) Lalle Allah a wurinsa ne (kaɗai) sanin lokacin tashin alƙiyama yake, kuma (Shi) Yake saukar da ruwa, (Shi) kuma Yake sane da abin da yake cikin mahaifa[1]; ba kuwa wani rai da yake sane da abin da zai aikata gobe, ba kuma wani rai da yake sane da ƙasar da zai mutu. Lalle Allah Shi ne Masani, Mai cikakken ilimi

(1) Watau ya san komai na halittarsa, tun daga lokacin shigarsa mahaifa har zuwa ma-komarsa ta qarshe.

Sura Sajda

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓمٓ ﴿١﴾ تَنزِيلُ ٱلْكِتَٰبِ لَا رَيْبَ فِيهِ مِن رَّبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ
﴿٢﴾ أَمْ يَقُولُونَ ٱفْتَرَىٰهُ ۚ بَلْ هُوَ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّكَ لِتُنذِرَ قَوْمًا
مَّآ أَتَىٰهُم مِّن نَّذِيرٍ مِّن قَبْلِكَ لَعَلَّهُمْ يَهْتَدُونَ ﴿٣﴾ ٱللَّهُ
ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ
ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ عَلَى ٱلْعَرْشِ ۖ مَا لَكُم مِّن دُونِهِۦ مِن وَلِىٍّ وَلَا شَفِيعٍ ۚ
أَفَلَا تَتَذَكَّرُونَ ﴿٤﴾ يُدَبِّرُ ٱلْأَمْرَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ إِلَى ٱلْأَرْضِ ثُمَّ يَعْرُجُ
إِلَيْهِ فِى يَوْمٍ كَانَ مِقْدَارُهُۥٓ أَلْفَ سَنَةٍ مِّمَّا تَعُدُّونَ ﴿٥﴾ ذَٰلِكَ
عَٰلِمُ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٦﴾ ٱلَّذِىٓ أَحْسَنَ
كُلَّ شَىْءٍ خَلَقَهُۥ ۖ وَبَدَأَ خَلْقَ ٱلْإِنسَٰنِ مِن طِينٍ ﴿٧﴾ ثُمَّ جَعَلَ
نَسْلَهُۥ مِن سُلَٰلَةٍ مِّن مَّآءٍ مَّهِينٍ ﴿٨﴾ ثُمَّ سَوَّىٰهُ وَنَفَخَ فِيهِ مِن
رُّوحِهِۦ ۖ وَجَعَلَ لَكُمُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ وَٱلْأَفْـِٔدَةَ ۚ قَلِيلًا
مَّا تَشْكُرُونَ ﴿٩﴾ وَقَالُوٓا۟ أَءِذَا ضَلَلْنَا فِى ٱلْأَرْضِ أَءِنَّا لَفِى
خَلْقٍ جَدِيدٍ ۚ بَلْ هُم بِلِقَآئِ رَبِّهِمْ كَٰفِرُونَ ﴿١٠﴾ قُلْ يَتَوَفَّىٰكُم
مَّلَكُ ٱلْمَوْتِ ٱلَّذِى وُكِّلَ بِكُمْ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُمْ تُرْجَعُونَ ﴿١١﴾

(1) ALIF LAM MIM[1].
(2) Saukar da Littafin da babu kokwanto a cikinsa daga Ubangijin talikai ne
(3) Ko kuwa suna cewa (Annabi Muhammadu) ƙirƙirar sa ya yi?" Ba haka ne ba, shi dai (Alƙur'ani) gaskiya ne daga Ubangijinka yake, don ka gargaɗi mutanen da wani mai gargaɗi bai zo musu gabaninka ba, don su shiriya
(4)Allah ne Wanda Ya halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu cikin kwana shida sannan Ya daidaita bisa Al'arshi; ba ku da wani majiɓincin al'amari ko mai ceto bayansa. Yanzu me ya sa ba kwa wa'azantuwa?
(5) Yana shirya al'amari daga sama zuwa ƙasa sannan (al'amarin) ya hau zuwa gare Shi a cikin wani yini da gwargwadon (tsawonsa) yake shekara dubu ne daga abin da kuke ƙirgawa
(6) Wannan (Shi ne) Masanin ɓoye da sarari, Mabuwayi, Mai rahama
(7) Wanda Ya kyautata kowane abu da ya halicce shi; kuma Ya fari halittar mutum daga taɓo
(8) Sannan Ya sanya zuriyarsa daga tataccen ruwa wulaƙantacce
(9) Sannan Ya daidaita shi, Ya kuma busa masa daga ruhinsa; kuma Ya sanya muku ji da gani da zukata. Kaɗan ne ƙwarai kuke godewa
(10) Suka kuma ce: "Yanzu idan muka zagwanye a cikin ƙasa, ashe za a sake sabunta halittarmu?" A'a, su dai suna kafircewa ne da saduwa da Ubangijinsu
(11) Ka ce (da su): "Mala'ikan mutuwa ne wanda aka wakilta muku zai karɓi ranku sannan kuma ga Ubangijinku za a komar da ku

(1) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8.

وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلْمُجْرِمُونَ نَاكِسُوا۟ رُءُوسِهِمْ عِندَ رَبِّهِمْ
رَبَّنَآ أَبْصَرْنَا وَسَمِعْنَا فَٱرْجِعْنَا نَعْمَلْ صَٰلِحًا إِنَّا مُوقِنُونَ
﴿١٢﴾ وَلَوْ شِئْنَا لَءَاتَيْنَا كُلَّ نَفْسٍ هُدَىٰهَا وَلَٰكِنْ حَقَّ
ٱلْقَوْلُ مِنِّى لَأَمْلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنَ ٱلْجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ أَجْمَعِينَ
﴿١٣﴾ فَذُوقُوا۟ بِمَا نَسِيتُمْ لِقَآءَ يَوْمِكُمْ هَٰذَآ إِنَّا نَسِينَٰكُمْ ۖ
وَذُوقُوا۟ عَذَابَ ٱلْخُلْدِ بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿١٤﴾ إِنَّمَا يُؤْمِنُ
بِـَٔايَٰتِنَا ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِّرُوا۟ بِهَا خَرُّوا۟ سُجَّدًا وَسَبَّحُوا۟ بِحَمْدِ
رَبِّهِمْ وَهُمْ لَا يَسْتَكْبِرُونَ ﴿١٥﴾ تَتَجَافَىٰ جُنُوبُهُمْ
عَنِ ٱلْمَضَاجِعِ يَدْعُونَ رَبَّهُمْ خَوْفًا وَطَمَعًا وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ
يُنفِقُونَ ﴿١٦﴾ فَلَا تَعْلَمُ نَفْسٌ مَّآ أُخْفِىَ لَهُم مِّن قُرَّةِ أَعْيُنٍ
جَزَآءًۢ بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٧﴾ أَفَمَن كَانَ مُؤْمِنًا كَمَن كَانَ فَاسِقًا ۚ
لَّا يَسْتَوُۥنَ ﴿١٨﴾ أَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَلَهُمْ
جَنَّٰتُ ٱلْمَأْوَىٰ نُزُلًۢا بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٩﴾ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ فَسَقُوا۟
فَمَأْوَىٰهُمُ ٱلنَّارُ ۖ كُلَّمَآ أَرَادُوٓا۟ أَن يَخْرُجُوا۟ مِنْهَآ أُعِيدُوا۟ فِيهَا
وَقِيلَ لَهُمْ ذُوقُوا۟ عَذَابَ ٱلنَّارِ ٱلَّذِى كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ﴿٢٠﴾

(12) Da kuwa za ka ga lokacin da masu manyan laifuka suke sunkuye da kawunansu a wurin Ubangiijnsu (suna cewa): “Ya Ubangijinmu, mun gani, mun kuma ji, to Ka mayar da mu (duniya), za mu yi aiki nagari, haƙiƙa mu masu sakankancewa ne.”

(13) Idan kuwa da Mun ga dama, tabbas da Mun bai wa kowane rai shiriyarsa, sai dai kuma maganata ta tabbata cewa, tabbas zan cike Jahannama da aljannu da mutane gaba ɗaya

(14) Sai (a ce da su): “Ku ɗanɗani (azaba) saboda mancewa da kuka yi da saduwa da wannan ranar taku, lalle Mu ma Mun yi watsi da ku; kuma ku ɗanɗani azaba mai ɗorewa saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa

(15) Lalle kawai masu imani da ayoyinmu su ne waɗanda idan aka yi musu wa’azi da su za su faɗi suna masu sujjada su kuma yi tasbihi tare da yabon Ubangijinsu, kuma su ba sa yin girman kai

(16) Kuyaƃunsu suna nesantar wuraren kwanciya[1], suna bauta wa Ubangijinsu cikin halin tsoro da kuma kwaɗayi, kuma suna ciyarwa daga abin da Muka arzuta su

(17) Kuma ba wani rai da zai san abin da aka ƃoye musu na faranta rai, don sakamako game da abin da suka kasance suna aikatawa

(18) Yanzu wanda ya zamanto mumini ya zama kamar wanda ya kasance fasiƙi? Ai ba za su zama daidai ba

(19) Amma waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, to suna da gidajen Aljanna na makoma, (wannan) liyafa ce saboda abin da suka kasance suna aikatawa

(20) Amma kuma waɗanda suka fice daga biyayyar Allah, to makomarsu wuta ce; ko da yaushe suka yi niyyar fitowa daga gare ta sai a mayar da su a cikinta a kuma ce da su: “Ku ɗanɗani azabar wuta wadda kuka kasance kuna ƙaryatawa.”

(1) Watau suna qaurace wa wuraren barci, suna tsayawa cikin dare suna sallolin nafilfilu suna roqon Allah ( ).

وَلَنُذِيقَنَّهُم مِّنَ ٱلْعَذَابِ ٱلْأَدْنَىٰ دُونَ ٱلْعَذَابِ ٱلْأَكْبَرِ
لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿٢١﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن ذُكِّرَ بِـَٔايَـٰتِ رَبِّهِۦ ثُمَّ
أَعْرَضَ عَنْهَآ ۚ إِنَّا مِنَ ٱلْمُجْرِمِينَ مُنتَقِمُونَ ﴿٢٢﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا
مُوسَى ٱلْكِتَـٰبَ فَلَا تَكُن فِى مِرْيَةٍ مِّن لِّقَآئِهِۦ ۖ وَجَعَلْنَـٰهُ
هُدًى لِّبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿٢٣﴾ وَجَعَلْنَا مِنْهُمْ أَئِمَّةً يَهْدُونَ بِأَمْرِنَا
لَمَّا صَبَرُوا۟ ۖ وَكَانُوا۟ بِـَٔايَـٰتِنَا يُوقِنُونَ ﴿٢٤﴾ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ
يَفْصِلُ بَيْنَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ فِيمَا كَانُوا۟ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ
﴿٢٥﴾ أَوَلَمْ يَهْدِ لَهُمْ كَمْ أَهْلَكْنَا مِن قَبْلِهِم مِّنَ ٱلْقُرُونِ
يَمْشُونَ فِى مَسَـٰكِنِهِمْ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَـٰتٍ ۖ أَفَلَا يَسْمَعُونَ
﴿٢٦﴾ أَوَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّا نَسُوقُ ٱلْمَآءَ إِلَى ٱلْأَرْضِ ٱلْجُرُزِ فَنُخْرِجُ
بِهِۦ زَرْعًا تَأْكُلُ مِنْهُ أَنْعَـٰمُهُمْ وَأَنفُسُهُمْ ۖ أَفَلَا يُبْصِرُونَ
﴿٢٧﴾ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَـٰذَا ٱلْفَتْحُ إِن كُنتُمْ صَـٰدِقِينَ ﴿٢٨﴾
قُلْ يَوْمَ ٱلْفَتْحِ لَا يَنفَعُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ إِيمَـٰنُهُمْ وَلَا هُمْ
يُنظَرُونَ ﴿٢٩﴾ فَأَعْرِضْ عَنْهُمْ وَٱنتَظِرْ إِنَّهُم مُّنتَظِرُونَ ﴿٣٠﴾

سُورَةُ الأَحْزَابِ

(21) Kuma tabbas lalle za Mu ɗandana musu (wani abu) daga azabar da ta fi ƙanƙanta (ta duniya) kafin azabar da ta fi girma (ta lahira) don su dawo (daga ɓata)

(22) Wane ne kuma mafi zalunci fiye da wanda aka yi wa wa'azi da ayoyin Ubangijinsa sannan ya bijire musu? Lalle Mu Masu saka wa masu manyan laifuka ne

(23) Haƙiƙa kuma Mu Mun bai wa Musa Littafi, to kada ka kasance (kai Manzo) cikin kokwanto na saduwa da shi (Musan)[1]. Kuma Mun sanya shi ya zamanto shiriya ga Banu-Isra'ila

(24) Muka kuma sanya shugabanni daga cikinsu waɗanda suke shiryuwa da umarninmu yayin da suka yi haƙuri, suka kuma kasance suna sakankancewa da ayoyinmu

(25) Lalle Ubangijinka Shi ne zai yi hukunci a tsakaninsu ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna sassaɓawa a kansa

(26) Yanzu ba su gane wa idanunsu ba al'ummu nawa Muka hallakar a gabaninsu waɗanda suke ta zirga-zirga tsakankanin gidajensu? Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi; to me ya sa ba sa sauraro ne?

(27) Ko kuwa ba sa gani cewa Mu Muke koro ruwa zuwa ga ƙeƙasasshiyar ƙasa, sai Mu fitar da tsirrai da shi, waɗanda dabbobinsu da su kansu suke ci daga gare shi? To me ya sa ba sa lura ne?

(28) Suna kuma cewa: "Yaushe ne (ranar) wannan hukuncin idan kun kasance masu gaskiya?

(29) Ka ce: "Ranar hukuncin, waɗanda suka kafirce, imaninsu ba zai amfane su ba, kuma ba ma za a saurara musu ba."

(30) To ka rabu da su, ka kuma saurara, lalle su ma masu sauraro ne

(1) Watau haxuwar Annabi Muhammad ( ) da Annabi Musa ( ) a daren mi'iraji.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ ٱتَّقِ ٱللَّهَ وَلَا تُطِعِ ٱلْكَٰفِرِينَ وَٱلْمُنَٰفِقِينَ ۚ إِنَّ
ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمًا ﴿١﴾ وَٱتَّبِعْ مَا يُوحَىٰٓ إِلَيْكَ
مِن رَّبِّكَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرًا ﴿٢﴾ وَتَوَكَّلْ
عَلَى ٱللَّهِ ۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلًا ﴿٣﴾ مَّا جَعَلَ ٱللَّهُ لِرَجُلٍ مِّن
قَلْبَيْنِ فِى جَوْفِهِۦ ۖ وَمَا جَعَلَ أَزْوَٰجَكُمُ ٱلَّٰٓـِٔى تُظَٰهِرُونَ
مِنْهُنَّ أُمَّهَٰتِكُمْ ۚ وَمَا جَعَلَ أَدْعِيَآءَكُمْ أَبْنَآءَكُمْ ۚ ذَٰلِكُمْ قَوْلُكُم
بِأَفْوَٰهِكُمْ ۖ وَٱللَّهُ يَقُولُ ٱلْحَقَّ وَهُوَ يَهْدِى ٱلسَّبِيلَ ﴿٤﴾
ٱدْعُوهُمْ لِءَابَآئِهِمْ هُوَ أَقْسَطُ عِندَ ٱللَّهِ ۚ فَإِن لَّمْ تَعْلَمُوٓا۟ ءَابَآءَهُمْ
فَإِخْوَٰنُكُمْ فِى ٱلدِّينِ وَمَوَٰلِيكُمْ ۚ وَلَيْسَ عَلَيْكُمْ جُنَاحٌ فِيمَآ
أَخْطَأْتُم بِهِۦ وَلَٰكِن مَّا تَعَمَّدَتْ قُلُوبُكُمْ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ
غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٥﴾ ٱلنَّبِىُّ أَوْلَىٰ بِٱلْمُؤْمِنِينَ مِنْ أَنفُسِهِمْ ۖ
وَأَزْوَٰجُهُۥٓ أُمَّهَٰتُهُمْ ۗ وَأُو۟لُوا۟ ٱلْأَرْحَامِ بَعْضُهُمْ أَوْلَىٰ بِبَعْضٍ
فِى كِتَٰبِ ٱللَّهِ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُهَٰجِرِينَ إِلَّآ أَن تَفْعَلُوٓا۟ إِلَىٰٓ
أَوْلِيَآئِكُم مَّعْرُوفًا ۚ كَانَ ذَٰلِكَ فِى ٱلْكِتَٰبِ مَسْطُورًا ﴿٦﴾

Sura Ahzab

(1) Ya kai wannan Annabi, ka kiyaye dokokin Allah, kada ka yi wa kafirai da munafukai da'a. Lalle Allah Ya kasance Masani ne, Mai hikima
(2) Kuma ka bi abin da ake yi maka wahayinsa daga Ubangijinka. Lalle Allah Ya kasance Masanin abin da kuke aikatawa ne
(3) Ka kuma dogara ga Allah. Allah kuwa Ya isa wakili
(4) Allah bai sanya wa wani mutum zuciya biyu ba a cikinsa. Kuma bai sanya matanku waɗanda kuke yi musu zihari[1] (su zama) iyayenku ba. Bai kuma sanya 'ya'yan rikonku (su zama) 'ya'yanku ba[2] . Wannan magana ce da kuke yi da bakunanku; Allah kuwa Yana faɗar gaskiya ne, kuma Shi ne Yake shiryarwa ga hanya (ta gaskiya)
(5) Ku danganta su ('ya'yan riko) ga iyayensu maza shi ne adalci a wur in Allah. Amma idan ba ku san iyayensu maza ba, to 'yan'uwanku ne a addini, kuma bararrun bayinku ne. Babu kuma laifi a kanku game da abin da kuka yi kuskuren yin sa, sai dai abin da zukatanku suka yi gangancin (aikatawa). Allah kuwa Ya kasance Mai gafara ne, Mai jin ƙai
(6) Annabi shi ya fi cancanta ga muminai fiye da kansu[3]; matansa kuma iyayensu ne. Dangi na zumunta kuma shashinsu ya fi kusanci daga wani shashi[4] a cikin Littafin Allah daga kusancin muminai da masu hijira, sai dai idan za ku aikata wani alheri ne ga masoyanku (muminai). Wannan ya kasance a rubuce a cikin Lauhul Mahafuzu

(1) Zihari, shi ne miji ya kwatanta matarsa da mahaifiyarsa wajen haramci. Wannan wata al'ada ce ta Larabawa a jahiliyya da Musulunci ya haramta ta.

(2) Gabanin zuwa Musulunci Larabawa sukan mayar da 'ya'yansu na riqo kamar 'ya'yan da suka haifa wajen hukunce-hukunce. Sai Allah ya haramta aikata haka.

(3) Watau shi ya fi cancanta su qaunace shi fiye da kawunansu.

(4) Watau dangi na zumunci su ne suka fi cancanta su ci gadon junansu.

وَإِذْ أَخَذْنَا مِنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مِيثَٰقَهُمْ وَمِنكَ وَمِن نُّوحٍ وَإِبْرَٰهِيمَ
وَمُوسَىٰ وَعِيسَى ٱبْنِ مَرْيَمَ ۖ وَأَخَذْنَا مِنْهُم مِّيثَٰقًا غَلِيظًا ۝٧
لِّيَسْـَٔلَ ٱلصَّٰدِقِينَ عَن صِدْقِهِمْ ۚ وَأَعَدَّ لِلْكَٰفِرِينَ عَذَابًا أَلِيمًا
۝٨ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱذْكُرُوا۟ نِعْمَةَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ إِذْ جَآءَتْكُمْ
جُنُودٌ فَأَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ رِيحًا وَجُنُودًا لَّمْ تَرَوْهَا ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ
بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرًا ۝٩ إِذْ جَآءُوكُم مِّن فَوْقِكُمْ وَمِنْ أَسْفَلَ
مِنكُمْ وَإِذْ زَاغَتِ ٱلْأَبْصَٰرُ وَبَلَغَتِ ٱلْقُلُوبُ ٱلْحَنَاجِرَ
وَتَظُنُّونَ بِٱللَّهِ ٱلظُّنُونَا۠ ۝١٠ هُنَالِكَ ٱبْتُلِىَ ٱلْمُؤْمِنُونَ وَزُلْزِلُوا۟
زِلْزَالًا شَدِيدًا ۝١١ وَإِذْ يَقُولُ ٱلْمُنَٰفِقُونَ وَٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم
مَّرَضٌ مَّا وَعَدَنَا ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ إِلَّا غُرُورًا ۝١٢ وَإِذْ قَالَت طَّآئِفَةٌ
مِّنْهُمْ يَٰٓأَهْلَ يَثْرِبَ لَا مُقَامَ لَكُمْ فَٱرْجِعُوا۟ ۚ وَيَسْتَـْٔذِنُ فَرِيقٌ
مِّنْهُمُ ٱلنَّبِىَّ يَقُولُونَ إِنَّ بُيُوتَنَا عَوْرَةٌ وَمَا هِىَ بِعَوْرَةٍ ۖ إِن يُرِيدُونَ
إِلَّا فِرَارًا ۝١٣ وَلَوْ دُخِلَتْ عَلَيْهِم مِّنْ أَقْطَارِهَا ثُمَّ سُئِلُوا۟ ٱلْفِتْنَةَ
لَـَٔاتَوْهَا وَمَا تَلَبَّثُوا۟ بِهَآ إِلَّا يَسِيرًا ۝١٤ وَلَقَدْ كَانُوا۟ عَٰهَدُوا۟
ٱللَّهَ مِن قَبْلُ لَا يُوَلُّونَ ٱلْأَدْبَٰرَ ۚ وَكَانَ عَهْدُ ٱللَّهِ مَسْـُٔولًا ۝١٥

(7) Kuma (ka tuna) lokacin da Muka rifki alkawura daga annabawa (na isar da aike), kuma daga gare ka, kuma daga Nuhu da Ibrahimu da Musa da Isa dan Maryamu; Muka kuma rifki alkawari mai kauri daga gare su

(8) Don (Allah) Ya tambayi masu gaskiya game da gaskiyarsu[1], Ya kuma tanadi azaba mai radadi ga kafirai

(9) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku tuna ni'imar Allah a gare ku lokacin da wasu rundunoni (na gangankon kafurai) suka zo muku, sai Muka aiko musu iska da wasu rundunoni da ba ku gan su ba[2]. Allah kuwa Ya kasance Mai ganin abin da kuke aikatawa ne

(10) A lokacin da suka zo muku ta samanku da ƙasanku, da kuma yayin da idanuwa suka kauce wa (ganin komai sai maƙiya), zukatanku kuma suka cika da tsoro kuka rifka zace-zace game da Allah

(11) A nan ne fa aka jarrabi muminai, aka kuma girgiza su girgizawa mai tsanani

(12) Kuma (ka tuna) lokacin da munafukai da waɗanda suke da cuta a zukatansu suke cewa: "Allah da Manzonsa ba wani alƙawarin da suka yi mana sai na rudi."

(13) Y Kuma (ka tuna) lokacin da wata jama'a daga cikinsu ta ce: "Ya ku mutanen Yasriba[3], ba ku da wurin zama, sai ku koma." Wata ƙungiya kuma daga cikinsu tana neman izinin Annabi da cewa: "Lalle gidajenmu tsirara tuƙwi suke," alhali kuwa ba tsirara tuƙwi suke ba; ba abin da suke nufi sai gudu

(14) Da kuwa za a shigo musu ta kowane ɓangare sannan a neme su da yin fitinar (komawa ga kafirci), to Wallahi da sun aikata (hakan) ba kuwa za su jinkirta da shi ba (wato kafircin) sai dan lokacin ƙankani

(15) Tun da can kuwa haƙiƙa sun yi wa Allah alƙawarin (cewa) ba za su ba da baya ba. Alƙawarin Allah kuwa ya kasance abin tambaya ne

(1) Watau ya tambati annabawa ko sun isar da saqon da ya aiko su da shi.

(2) Watau su ne rundunonin kafiran Quraishawa da qawayensu waxanda suka nufo Madina a shekara ta 5 don su yaqi Musulmi, amma Allah ya karya su.

(3) Yasrib, tsohon sunan Madina ne tun gabanin Musulunci. Annabi ya canja shi zuwa Madina.

قُل لَّن يَنفَعَكُمُ ٱلْفِرَارُ إِن فَرَرْتُم مِّنَ ٱلْمَوْتِ أَوِ ٱلْقَتْلِ وَإِذًا
لَّا تُمَتَّعُونَ إِلَّا قَلِيلًا ﴿١٦﴾ قُلْ مَن ذَا ٱلَّذِى يَعْصِمُكُم مِّنَ ٱللَّهِ
إِنْ أَرَادَ بِكُمْ سُوٓءًا أَوْ أَرَادَ بِكُمْ رَحْمَةً ۚ وَلَا يَجِدُونَ لَهُم مِّن دُونِ
ٱللَّهِ وَلِيًّا وَلَا نَصِيرًا ﴿١٧﴾ ۞ قَدْ يَعْلَمُ ٱللَّهُ ٱلْمُعَوِّقِينَ مِنكُمْ وَٱلْقَآئِلِينَ
لِإِخْوَٰنِهِمْ هَلُمَّ إِلَيْنَا ۖ وَلَا يَأْتُونَ ٱلْبَأْسَ إِلَّا قَلِيلًا ﴿١٨﴾ أَشِحَّةً
عَلَيْكُمْ ۖ فَإِذَا جَآءَ ٱلْخَوْفُ رَأَيْتَهُمْ يَنظُرُونَ إِلَيْكَ تَدُورُ أَعْيُنُهُمْ
كَٱلَّذِى يُغْشَىٰ عَلَيْهِ مِنَ ٱلْمَوْتِ ۖ فَإِذَا ذَهَبَ ٱلْخَوْفُ سَلَقُوكُم
بِأَلْسِنَةٍ حِدَادٍ أَشِحَّةً عَلَى ٱلْخَيْرِ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ لَمْ يُؤْمِنُوا۟ فَأَحْبَطَ
ٱللَّهُ أَعْمَٰلَهُمْ ۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرًا ﴿١٩﴾ يَحْسَبُونَ
ٱلْأَحْزَابَ لَمْ يَذْهَبُوا۟ ۖ وَإِن يَأْتِ ٱلْأَحْزَابُ يَوَدُّوا۟ لَوْ أَنَّهُم
بَادُونَ فِى ٱلْأَعْرَابِ يَسْـَٔلُونَ عَنْ أَنۢبَآئِكُمْ ۖ وَلَوْ كَانُوا۟ فِيكُم
مَّا قَٰتَلُوٓا۟ إِلَّا قَلِيلًا ﴿٢٠﴾ لَّقَدْ كَانَ لَكُمْ فِى رَسُولِ ٱللَّهِ أُسْوَةٌ حَسَنَةٌ
لِّمَن كَانَ يَرْجُوا۟ ٱللَّهَ وَٱلْيَوْمَ ٱلْءَاخِرَ وَذَكَرَ ٱللَّهَ كَثِيرًا ﴿٢١﴾
وَلَمَّا رَءَا ٱلْمُؤْمِنُونَ ٱلْأَحْزَابَ قَالُوا۟ هَٰذَا مَا وَعَدَنَا ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ
وَصَدَقَ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ ۚ وَمَا زَادَهُمْ إِلَّآ إِيمَٰنًا وَتَسْلِيمًا ﴿٢٢﴾

(16) Ka ce: “In kuna guje wa mutuwa ne ko kisa, to gudun ba zai amfane ku ba, a yayin nan kuwa ba za a jiyar da ku wani dadi ba sai dan kadan.”
(17) Ka ce: “Wane ne zai kare ku daga Allah idan Ya nufe ku da wani mummunan abu ko kuma Ya nufe ku da wata rahama?” Ba kuma za su sama wa kansu wani majiɓinci ko mai taimako ba in ba Allah ba
(18) Haƙiƙa Allah Yana sane da masu hana ruwa gudu[1] daga cikinku, da masu ce wa ‘yan’uwansu: “Ku zo wurinmu,” kuma ba sa zuwa yaƙi sai kadan
(19) (Su ne) masu yi muku rowar (taimako); sannan idan (abin) tsoro ya zo, sai ka gan su suna duban ka idanuwansu suna jujjuyawa kamar wanda yake suman mutuwa; sannan idan tsoron ya yaye, sai su rika cutar da ku da harsuna kaifafa, suna masu rowar alheri. Wadannan ba su yi imani ba, don haka Allah Ya lalata ayyukansu. Wannan kuwa ya kasance abu ne mai sauki a wurin Allah
(20) Suna zaton rundunonin gangami ba su tafi ba; da a ce kuwa rundunonin na gangami za su sake dawowa to da sai su rika burin ina ma suna can tare da mutanen ƙauye suna tambayar labaranku; ko ma da za su kasance a cikinku to da ba za su yi yaki ba sai dan kadan
(21) Ciertamente, en el Mensajero de Al-lah hay un buen ejemplo para todo aƙuel ƙue espera el encuentro con su Señor y el Último Día (con temor y anhelo) y glorifica mucho a Al-lah.
(22) Lokacin kuwa da muminai suka ga rundunonin gangami sai suka ce: “Wannan shi ne abin da Allah da Manzonsa suka yi mana alƙawari, Allah kuwa da Manzonsa sun yi gaskiya. Ba kuwa abin da (wannan) ya ƙara musu sai imani da miƙa wuya

(1) Su ne munafukai masu daqile Musulmi da karya musu gwiwa wajen fita yaqi.

مِّنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ رِجَالٌ صَدَقُوا۟ مَا عَٰهَدُوا۟ ٱللَّهَ عَلَيْهِ ۖ فَمِنْهُم مَّن
قَضَىٰ نَحْبَهُۥ وَمِنْهُم مَّن يَنتَظِرُ ۖ وَمَا بَدَّلُوا۟ تَبْدِيلًا ﴿٢٣﴾ لِّيَجْزِىَ
ٱللَّهُ ٱلصَّٰدِقِينَ بِصِدْقِهِمْ وَيُعَذِّبَ ٱلْمُنَٰفِقِينَ إِن شَآءَ أَوْ
يَتُوبَ عَلَيْهِمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٢٤﴾ وَرَدَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ بِغَيْظِهِمْ لَمْ يَنَالُوا۟ خَيْرًا ۚ وَكَفَى ٱللَّهُ ٱلْمُؤْمِنِينَ
ٱلْقِتَالَ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ قَوِيًّا عَزِيزًا ﴿٢٥﴾ وَأَنزَلَ ٱلَّذِينَ ظَٰهَرُوهُم مِّنْ
أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ مِن صَيَاصِيهِمْ وَقَذَفَ فِى قُلُوبِهِمُ ٱلرُّعْبَ
فَرِيقًا تَقْتُلُونَ وَتَأْسِرُونَ فَرِيقًا ﴿٢٦﴾ وَأَوْرَثَكُمْ أَرْضَهُمْ
وَدِيَٰرَهُمْ وَأَمْوَٰلَهُمْ وَأَرْضًا لَّمْ تَطَـُٔوهَا ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ
شَىْءٍ قَدِيرًا ﴿٢٧﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِىُّ قُل لِّأَزْوَٰجِكَ إِن كُنتُنَّ تُرِدْنَ
ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا وَزِينَتَهَا فَتَعَالَيْنَ أُمَتِّعْكُنَّ وَأُسَرِّحْكُنَّ
سَرَاحًا جَمِيلًا ﴿٢٨﴾ وَإِن كُنتُنَّ تُرِدْنَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَٱلدَّارَ
ٱلْءَاخِرَةَ فَإِنَّ ٱللَّهَ أَعَدَّ لِلْمُحْسِنَٰتِ مِنكُنَّ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿٢٩﴾
يَٰنِسَآءَ ٱلنَّبِىِّ مَن يَأْتِ مِنكُنَّ بِفَٰحِشَةٍ مُّبَيِّنَةٍ يُضَٰعَفْ
لَهَا ٱلْعَذَابُ ضِعْفَيْنِ ۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرًا ﴿٣٠﴾

(23) Akwai wasu mazaje daga muminai da suka cika abin da suka yi wa Allah alƙawari da shi; akwai daga cikinsu wanda ya haɗu da ajalinsa, akwai kuma daga cikinsu wanda yake sauraron (ajalin); kuma ba su yi kowace irin sabawa ba (game da alƙawarin)

(24) Don Allah Ya saka wa masu gaskiya a kan gaskiyarsu, Ya kuma azabtar da munafukai idan Ya ga dama, ko kuma Ya karɓi tubarsu. Lalle Allah Ya kasance Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(25) Allah kuma Ya komar da waɗanda suka kafirta da fushinsu ba su sami wani alheri ba. Allah kuma Ya ɗauke wa muminai yin yaƙi. Domin kuwa Allah Ya kasance Mai ƙarfi ne, Mabuwayi

(26) Ya kuma sauko da waɗanda suka taimake su daga ma'abota littafi[1] daga ganuwoyinsu Ya kuma jefa tsoro a zukatansu, wasu jama'ar kuke kashe su kuna kuma ribace wasu jama'ar

(27) Ya kuma gadar muku ƙasarsu da gidajensu da dukiyoyinsu, da kuma wata ƙasa ma da ba ku taɓa taka ta ba[2]. Allah kuwa Ya kasance Mai iko ne a kan komai

(28) ¡Ya kai wannan Annabi, ka gaya wa matanka: "Idan kun kasance kuna son rayuwar duniya ne da kuma adonta, to sai ku zo in jiyar da ku dadi, in kuma sake ku kyakkyawan saki

(29) "Idan kuwa kun kasance kuna ƙaunar Allah ne da Manzonsa da kuma ranar lahira, to haƙiƙa Allah Ya tanadi lada mai girma ga masu kyautatawa daga cikinku

(30) Ya ku matan Annabi, duk wadda ta zo da wani abin ƙi na sarari daga cikinku to za a ninninka mata azaba ninki biyu. Yin wannan kuma ya kasance abu ne mai sauƙi ga Allah

(1) Watau Yahudawan Banu Quraiza. Ya sauko da su daga ganuwoyinsu da suka tanada don kare kansu.

(2) Watau ita ce qasar Khaibar wadda Musulmi suka samu bayan shekara ta biyu da gama yaqin Ahzab.



وَمَن يَقْنُتْ مِنكُنَّ لِلَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَتَعْمَلْ صَٰلِحًا نُّؤْتِهَآ
أَجْرَهَا مَرَّتَيْنِ وَأَعْتَدْنَا لَهَا رِزْقًا كَرِيمًا ﴿٣١﴾ يَٰنِسَآءَ ٱلنَّبِىِّ
لَسْتُنَّ كَأَحَدٍ مِّنَ ٱلنِّسَآءِ إِنِ ٱتَّقَيْتُنَّ فَلَا تَخْضَعْنَ بِٱلْقَوْلِ
فَيَطْمَعَ ٱلَّذِى فِى قَلْبِهِۦ مَرَضٌ وَقُلْنَ قَوْلًا مَّعْرُوفًا ﴿٣٢﴾ وَقَرْنَ
فِى بُيُوتِكُنَّ وَلَا تَبَرَّجْنَ تَبَرُّجَ ٱلْجَٰهِلِيَّةِ ٱلْأُولَىٰ ۖ وَأَقِمْنَ
ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتِينَ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَطِعْنَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ ۚ إِنَّمَا
يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيُذْهِبَ عَنكُمُ ٱلرِّجْسَ أَهْلَ ٱلْبَيْتِ وَيُطَهِّرَكُمْ
تَطْهِيرًا ﴿٣٣﴾ وَٱذْكُرْنَ مَا يُتْلَىٰ فِى بُيُوتِكُنَّ مِنْ
ءَايَٰتِ ٱللَّهِ وَٱلْحِكْمَةِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ لَطِيفًا خَبِيرًا ﴿٣٤﴾
إِنَّ ٱلْمُسْلِمِينَ وَٱلْمُسْلِمَٰتِ وَٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ
وَٱلْقَٰنِتِينَ وَٱلْقَٰنِتَٰتِ وَٱلصَّٰدِقِينَ وَٱلصَّٰدِقَٰتِ وَٱلصَّٰبِرِينَ
وَٱلصَّٰبِرَٰتِ وَٱلْخَٰشِعِينَ وَٱلْخَٰشِعَٰتِ وَٱلْمُتَصَدِّقِينَ
وَٱلْمُتَصَدِّقَٰتِ وَٱلصَّٰٓئِمِينَ وَٱلصَّٰٓئِمَٰتِ وَٱلْحَٰفِظِينَ
فُرُوجَهُمْ وَٱلْحَٰفِظَٰتِ وَٱلذَّٰكِرِينَ ٱللَّهَ كَثِيرًا
وَٱلذَّٰكِرَٰتِ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُم مَّغْفِرَةً وَأَجْرًا عَظِيمًا ﴿٣٥﴾

(31) Duk kuwa wadda ta yi biyayya ga Allah da Manzonsa daga cikinku ta kuma yi aiki nagari, to za Mu ba ta ladanta sau biyu, kuma Mun tanadar mata arziki mai girma

(32) Ya ku matan Annabi, ku fa ba kamar sauran mata kuke ba. Idan kun kiyaye dokokin Allah, to kada ku tausasa murya har yadda wani mai raunin imani a zuciyarsa zai yi kwaɗayin (wani abu), kuma ku yi Magana irin maganar da ta dace da shari'a

(33) Ku kuma zauna a cikin gidajenku, kada kuma ku rika fita (da bayyana ado) irin ta jahiliyyar farko; ku kuma tsayar da salla, ku ba da zakka, ku kuma bi Allah da Manzonsa. Abin da Allah Yake nufi kawai shi ne Ya kawar muku da duk wata ƙazanta, ya ku iyalin gidan Annabi, Ya kuma tsarkake ku tsarkakewa

(34) Kuma ku tuna abin da ake karantawa a cikin gidajenku na ayoyin Allah da kuma hikima. Lalle Allah Ya kasance Mai tausayawa ne, Masani

(35) Lalle Musulmi maza da Musulmi mata, da muminai maza da muminai mata, da masu biyayya maza da masu biyayya mata, da masu gaskiya maza da masu gaskiya mata, da masu haƙuri maza da masu haƙuri mata, da masu ƙasƙantar da kai maza da masu ƙasƙantar da kai mata, da masu sadaka maza da masu sadaka mata, da masu azumi maza da masu azumi mata, da maza masu kiyaye farjinsu da mata masu kiyaye farjinsu, da maza masu ambaton Allah da yawa da mata masu ambaton Allah (da yawa, dukkaninsu) Allah ya tanadar musu gafara da lada mai girma

وَمَا كَانَ لِمُؤْمِنٍ وَلَا مُؤْمِنَةٍ إِذَا قَضَى ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ أَمْرًا أَن يَكُونَ
لَهُمُ ٱلْخِيَرَةُ مِنْ أَمْرِهِمْ ۗ وَمَن يَعْصِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَقَدْ ضَلَّ ضَلَٰلًا
مُّبِينًا ﴿٣٦﴾ وَإِذْ تَقُولُ لِلَّذِىٓ أَنْعَمَ ٱللَّهُ عَلَيْهِ وَأَنْعَمْتَ عَلَيْهِ
أَمْسِكْ عَلَيْكَ زَوْجَكَ وَٱتَّقِ ٱللَّهَ وَتُخْفِى فِى نَفْسِكَ مَا ٱللَّهُ
مُبْدِيهِ وَتَخْشَى ٱلنَّاسَ وَٱللَّهُ أَحَقُّ أَن تَخْشَىٰهُ ۖ فَلَمَّا قَضَىٰ زَيْدٌ
مِّنْهَا وَطَرًا زَوَّجْنَٰكَهَا لِكَىْ لَا يَكُونَ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ حَرَجٌ فِىٓ
أَزْوَٰجِ أَدْعِيَآئِهِمْ إِذَا قَضَوْا۟ مِنْهُنَّ وَطَرًا ۚ وَكَانَ أَمْرُ ٱللَّهِ مَفْعُولًا
﴿٣٧﴾ مَّا كَانَ عَلَى ٱلنَّبِىِّ مِنْ حَرَجٍ فِيمَا فَرَضَ ٱللَّهُ لَهُۥ ۖ سُنَّةَ ٱللَّهِ فِى
ٱلَّذِينَ خَلَوْا۟ مِن قَبْلُ ۚ وَكَانَ أَمْرُ ٱللَّهِ قَدَرًا مَّقْدُورًا ﴿٣٨﴾ ٱلَّذِينَ
يُبَلِّغُونَ رِسَٰلَٰتِ ٱللَّهِ وَيَخْشَوْنَهُۥ وَلَا يَخْشَوْنَ أَحَدًا إِلَّا ٱللَّهَ ۗ وَكَفَىٰ
بِٱللَّهِ حَسِيبًا ﴿٣٩﴾ مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٍ مِّن رِّجَالِكُمْ وَلَٰكِن
رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمًا ﴿٤٠﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱذْكُرُوا۟ ٱللَّهَ ذِكْرًا كَثِيرًا ﴿٤١﴾ وَسَبِّحُوهُ
بُكْرَةً وَأَصِيلًا ﴿٤٢﴾ هُوَ ٱلَّذِى يُصَلِّى عَلَيْكُمْ وَمَلَٰٓئِكَتُهُۥ
لِيُخْرِجَكُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ ۚ وَكَانَ بِٱلْمُؤْمِنِينَ رَحِيمًا ﴿٤٣﴾

(36) Bai kamata ga wani mumini ko wata mumina ba, idan Allah da Manzonsa suka yi hukunci a kan wani al'amari su zama suna da wani zaɓi game da al'amarinsu. Wanda kuwa ya saba wa Allah da Manzonsa, to haƙiƙa ya ɓata, bayyanannen ɓata

(37) ﷺ(Ka tuna) lokacin da kake ce wa wannan da Allah Ya yi wa ni'ima, kai ma ka yi masa ni'ima[1]: "Riƙe matarka, kuma ka kiyaye dokokin Allah", alhali kuwa kana ɓoyewa a cikin ranka abin da Allah zai bayyana shi, kana kuma tsoron mutane[2], alhali kuma Allah ne Ya fi cancanta ka ji tsoron Sa; to lokacin da Zaidu ya gama buƙatarsa da ita (matarsa Zainab), Mun aurar maka ita, don saboda kada ya zama akwai ƙuntatawa ga muminai game da (auren) matan 'ya'yansu na riƙo lokacin da suka gama bukata da su. Al'amarin Allah kuwa ya kasance abin zartarwa ne

(38) Babu wani laifi a kan Annabi game da abin da Allah Ya halatta masa; (wannan kuwa) Sunnar Allah ce ga waɗanda suka gabace ka (daga annabawa). Al'amarin Allah kuwa ya kasance mai tabbata ne ba makawa

(39) Waɗanda suke isar da saƙon Allah suke kuma tsoron Sa, ba sa kuwa tsoron kowa sai Allah. Allah kuwa Ya isa Mai yin hisabi

(40) (Annabi) Muhammadu bai kasance uban ɗaya daga cikin mazajenku ba, sai dai (shi) ya kasance Manzon Allah ne kuma cikamakin annabawa. Allah kuma Ya kasance Masanin komai ne

(41) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ambaci Allah ambato mai yawa

(42) Kuma ku yi tasbihi a gare Shi safe da yamma

(43) Shi ne wanda Yake yi muku salati da mala'ikunsa don Ya fitar da ku daga duffai zuwa haske, Allah kuwa Ya kasance Mai rahama ga muminai

(1) Shi ne Zaidu xan Harisa da Annabi ( ) ya 'yanta shi, ya aura masa Zainab 'yar Jahshi ( ).

(2) Watau tsoron abin da mutane za su riqa faxa na cewa ya auri matar xansa na riqo.

تَحِيَّتُهُمْ يَوْمَ يَلْقَوْنَهُۥ سَلَٰمٌ ۚ وَأَعَدَّ لَهُمْ أَجْرًا كَرِيمًا ﴿٤٤﴾ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلنَّبِيُّ إِنَّآ أَرْسَلْنَٰكَ شَٰهِدًا وَمُبَشِّرًا وَنَذِيرًا ﴿٤٥﴾ وَدَاعِيًا
إِلَى ٱللَّهِ بِإِذْنِهِۦ وَسِرَاجًا مُّنِيرًا ﴿٤٦﴾ وَبَشِّرِ ٱلْمُؤْمِنِينَ بِأَنَّ لَهُم
مِّنَ ٱللَّهِ فَضْلًا كَبِيرًا ﴿٤٧﴾ وَلَا تُطِعِ ٱلْكَٰفِرِينَ وَٱلْمُنَٰفِقِينَ
وَدَعْ أَذَىٰهُمْ وَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِ ۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلًا ﴿٤٨﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِذَا نَكَحْتُمُ ٱلْمُؤْمِنَٰتِ ثُمَّ طَلَّقْتُمُوهُنَّ
مِن قَبْلِ أَن تَمَسُّوهُنَّ فَمَا لَكُمْ عَلَيْهِنَّ مِنْ عِدَّةٍ تَعْتَدُّونَهَا ۖ
فَمَتِّعُوهُنَّ وَسَرِّحُوهُنَّ سَرَاحًا جَمِيلًا ﴿٤٩﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ
إِنَّآ أَحْلَلْنَا لَكَ أَزْوَٰجَكَ ٱلَّٰتِىٓ ءَاتَيْتَ أُجُورَهُنَّ وَمَا مَلَكَتْ
يَمِينُكَ مِمَّآ أَفَآءَ ٱللَّهُ عَلَيْكَ وَبَنَٰتِ عَمِّكَ وَبَنَٰتِ عَمَّٰتِكَ
وَبَنَٰتِ خَالِكَ وَبَنَٰتِ خَٰلَٰتِكَ ٱلَّٰتِى هَاجَرْنَ مَعَكَ وَٱمْرَأَةً
مُّؤْمِنَةً إِن وَهَبَتْ نَفْسَهَا لِلنَّبِىِّ إِنْ أَرَادَ ٱلنَّبِىُّ أَن يَسْتَنكِحَهَا
خَالِصَةً لَّكَ مِن دُونِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ۖ قَدْ عَلِمْنَا مَا فَرَضْنَا
عَلَيْهِمْ فِىٓ أَزْوَٰجِهِمْ وَمَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُهُمْ لِكَيْلَا
يَكُونَ عَلَيْكَ حَرَجٌ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٥٠﴾

(44) Gaisuwarsu a ranar da za su haɗu da Shi (ita ce) 'Salamun Alaikum'. Ya kuma tanadar musu da lada na karamci

(45) Ya kai wannan Annabi, lalle Mu Mun aiko ka kana mai shaida, kuma mai albishir kuma mai gargaɗi

(46) Kuma mai kira zuwa ga Allah da izininsa, kuma fitila mai haskakawa

(47) Ka kuma yi wa muminai albishir cewa, suna da wata falala mai girma daga wurin Allah


(48) Kada kuma ka yi wa kafirai da munafukai ɗa'a, ka kuma bar cutarsu (da suke yi maka), ka kuma dogara ga Allah. Allah kuwa Ya isa Ya zama abin dogara

(49) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka auri mata muminai, sannan kuka sake su tun kafin ku sadu da su, to babu wata idda taku a kansu da za ku nemi cikar adadin (kwanakinta); sai ku jiyar da su dadi[1], kuma ku sake su kyakkyawan saki

(50) Ya kai wannan Annabi, lalle Mun halatta maka matanka waɗanda ka ba da sadakinsu, da kuma kuyanginka daga abin da Allah Ya ba ka na ganima, da 'ya'yan baffanka mata da 'ya'yan gwaggwaninka mata da 'ya'yan kawunka mata, da 'ya'yan yagwalgwalanka mata waɗanda suka yi hijira tare da kai, da kuma duk wata mace mumina, idan ta ba da kanta ga Annabi (shi) Annabin kuwa yana nufin ya aure ta, (wannan) kebantacce ne a gare ka[2], ban da sauran muminai. Hakika Mun san abin da Muka ɗora musu game da matansu da kuma kuyanginsu, don kada a samu wata ƙuntatawa a kanka. Allah kuwa Ya kasance Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(1) Watau su ba su abin da zai daxaxa musu rai, don ya rage musu raxaxin sakin da aka yi musu.

(2) Allah ( ) ya halatta wa Annabi ( ) auren duk wata mace mumina wadda za ta ba da kanta kyauta a gare shi ba tare da sadaki ba.


* تُرۡجِي مَن تَشَآءُ مِنۡهُنَّ وَتُـٔۡوِيٓ إِلَيۡكَ مَن تَشَآءُۖ وَمَنِ ٱبۡتَغَيۡتَ
مِمَّنۡ عَزَلۡتَ فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡكَۚ ذَٰلِكَ أَدۡنَىٰٓ أَن تَقَرَّ أَعۡيُنُهُنَّ
وَلَا يَحۡزَنَّ وَيَرۡضَيۡنَ بِمَآ ءَاتَيۡتَهُنَّ كُلُّهُنَّۚ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ
مَا فِي قُلُوبِكُمۡۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَلِيمًا ٥١ لَّا يَحِلُّ لَكَ
ٱلنِّسَآءُ مِنۢ بَعۡدُ وَلَآ أَن تَبَدَّلَ بِهِنَّ مِنۡ أَزۡوَٰجٖ وَلَوۡ أَعۡجَبَكَ
حُسۡنُهُنَّ إِلَّا مَا مَلَكَتۡ يَمِينُكَۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ
شَيۡءٖ رَّقِيبًا ٥٢ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَدۡخُلُواْ بُيُوتَ ٱلنَّبِيِّ
إِلَّآ أَن يُؤۡذَنَ لَكُمۡ إِلَىٰ طَعَامٍ غَيۡرَ نَٰظِرِينَ إِنَىٰهُ وَلَٰكِنۡ
إِذَا دُعِيتُمۡ فَٱدۡخُلُواْ فَإِذَا طَعِمۡتُمۡ فَٱنتَشِرُواْ وَلَا مُسۡتَـٔۡنِسِينَ
لِحَدِيثٍۚ إِنَّ ذَٰلِكُمۡ كَانَ يُؤۡذِي ٱلنَّبِيَّ فَيَسۡتَحۡيِۦ مِنكُمۡۖ
وَٱللَّهُ لَا يَسۡتَحۡيِۦ مِنَ ٱلۡحَقِّۚ وَإِذَا سَأَلۡتُمُوهُنَّ مَتَٰعٗا فَسۡـَٔلُوهُنَّ
مِن وَرَآءِ حِجَابٖۚ ذَٰلِكُمۡ أَطۡهَرُ لِقُلُوبِكُمۡ وَقُلُوبِهِنَّۚ
وَمَا كَانَ لَكُمۡ أَن تُؤۡذُواْ رَسُولَ ٱللَّهِ وَلَآ أَن تَنكِحُوٓاْ أَزۡوَٰجَهُۥ
مِنۢ بَعۡدِهِۦٓ أَبَدًاۚ إِنَّ ذَٰلِكُمۡ كَانَ عِندَ ٱللَّهِ عَظِيمًا ٥٣
إِن تُبۡدُواْ شَيۡـًٔا أَوۡ تُخۡفُوهُ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمًا ٥٤

(51) Ka dakatar da duk wadda ka ga dama daga cikinsu, ka kuma jawo duk wadda ka ga dama[1]; (duk) wadda kuwa ka nema daga waɗanda ka dakatar, to babu wani laifi a kanka. (Yin) wannan kuwa shi ya fi kusantar da kwanciyar ransu da kuma rashin yin baƙin ciki, su kuma yarda da duk abin da ka ba su dukkansu[2]. Allah kuwa Yana sane da abin da yake cikin zukatanku. Allah kuwa Ya kasance Masani ne, Mai haƙuri

(52) Bayan (waɗannan) wasu mata ba su halatta gare ka ba, ko kuma ka musanya waɗansu (matan) da su, ko da kuwa kyansu ya ƙayatar da kai, sai dai abin da ka mallaka na kuyangi. Allah kuwa Ya kasance Mai lura ne da komai

(53) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku shiga gidajen Annabi sai idan an yi muku izini zuwa (cin) abinci, alhali ba tare da kuna jiran dahuwarsa ba, sai dai kuma idan aka kira ku, to ku shiga, sannan idan kuka ci sai ku fice, ba tare da yin wata hira ta ɗebe kewa ba. Lalle wannan ya kasance yana cutar Annabi, sai yakan ji kunyar ku; Allah kuwa ba Ya jin kunyar (faɗar) gaskiya. Idan kuma za ku tambaye su (wato matan Annabi) wani abu na amfani, sai ku tambaye su ta bayan shamaki. Yin wannan shi ya fi tsarki ga zukatanku da kuma zukatansu. Kuma bai kamace ku ba ku cuci Manzon Allah ko kuma ku auri matansa a bayansa har abada. Lalle (yin) wannan ya kasance abu mai girma a wurin Allah

(54) Idan kuma kuka bayyana wani abu ko kuka ɓoye shi, to Allah Ya kasance Masanin komai ne

(1) Watau Allah ( ) bai wajabta masa rabon kwana a tsakanin matansa ba, yana iya dakatar da kwanan wadda ya ga dama ko ya jawo da kwananta.

(2) Domin sun tabbatar ba zai hana musu haqqoqinsu ba ko ya qi yi musu adalci.

لَّا جُنَاحَ عَلَيْهِنَّ فِيٓ ءَابَآئِهِنَّ وَلَآ أَبْنَآئِهِنَّ وَلَآ إِخْوَٰنِهِنَّ وَلَآ
أَبْنَآءِ إِخْوَٰنِهِنَّ وَلَآ أَبْنَآءِ أَخَوَٰتِهِنَّ وَلَا نِسَآئِهِنَّ وَلَا مَا مَلَكَتْ
أَيْمَٰنُهُنَّ ۚ وَٱتَّقِينَ ٱللَّهَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ شَهِيدًا
﴿٥٥﴾ إِنَّ ٱللَّهَ وَمَلَٰٓئِكَتَهُۥ يُصَلُّونَ عَلَى ٱلنَّبِىِّ ۚ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ صَلُّوا۟ عَلَيْهِ وَسَلِّمُوا۟ تَسْلِيمًا ﴿٥٦﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُؤْذُونَ
ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ لَعَنَهُمُ ٱللَّهُ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ وَأَعَدَّ لَهُمْ عَذَابًا
مُّهِينًا ﴿٥٧﴾ وَٱلَّذِينَ يُؤْذُونَ ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ بِغَيْرِ
مَا ٱكْتَسَبُوا۟ فَقَدِ ٱحْتَمَلُوا۟ بُهْتَٰنًا وَإِثْمًا مُّبِينًا ﴿٥٨﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِىُّ قُل لِّأَزْوَٰجِكَ وَبَنَاتِكَ وَنِسَآءِ ٱلْمُؤْمِنِينَ
يُدْنِينَ عَلَيْهِنَّ مِن جَلَٰبِيبِهِنَّ ۚ ذَٰلِكَ أَدْنَىٰٓ أَن يُعْرَفْنَ فَلَا
يُؤْذَيْنَ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٥٩﴾ لَّئِن لَّمْ يَنتَهِ ٱلْمُنَٰفِقُونَ
وَٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ وَٱلْمُرْجِفُونَ فِى ٱلْمَدِينَةِ
لَنُغْرِيَنَّكَ بِهِمْ ثُمَّ لَا يُجَاوِرُونَكَ فِيهَآ إِلَّا قَلِيلًا ﴿٦٠﴾ مَّلْعُونِينَ ۖ
أَيْنَمَا ثُقِفُوٓا۟ أُخِذُوا۟ وَقُتِّلُوا۟ تَقْتِيلًا ﴿٦١﴾ سُنَّةَ ٱللَّهِ فِى
ٱلَّذِينَ خَلَوْا۟ مِن قَبْلُ ۖ وَلَن تَجِدَ لِسُنَّةِ ٱللَّهِ تَبْدِيلًا ﴿٦٢﴾

(55) Babu laifi a kansu (matan) game da iyayensu maza (su gan su kuma su yi magana da su ba tare da shamaki ba) da kuma ‘ya’yansu maza da ‘ya’uwansu da ‘ya’yan ‘yan’uwansu maza da ‘ya’yan ‘yan’uwansu mata, da kuma matansu da bayinsu. Ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Ya kasance Mai ganin komai ne

(56) Lalle Allah da mala’ikunsa suna yin salati ga Annabi. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi salati a gare shi, kuma ku yi sallama mai yawa

(57) Lalle waɗanda suke cutar Allah da Manzonsa, to Allah Ya la’ance su a duniya da lahira, Ya kuma tanadar musu azaba mai wulaƙantarwa

(58) Waɗanda suke cutar muminai maza da muminai mata ba tare da sun yi laifi ba, to haƙiƙa sun ɗauki nauyin ƙage da kuma zunubi bayyananne

(59) Ya kai wannan Annabi, faɗa wa matanka da ‘ya’yanka mata da kuma matan muminai (cewa) su sanya lullubinsu. Wannan shi ya fi sanya wa a gane su[1], don kada a cuce su. Allah kuma Ya kasance Mai gafara ne, Mai rahama

(60) Tabbas munafukai da waɗanda suke da raunin imani a zukatansu da kuma masu yaɗa ƙarairayi a Madina, idan ba su bari ba, lalle za Mu cuna ka a kansu (don ka hukunta su), sannan kuma ba za su zauna da kai a cikinta ba sai ɗan lokaci ƙanƙani

(61) (Su) la’anannu ne; duk inda aka gamu da su a kama su, kuma a yi musu mummunan kisa

(62) (Wannan) Sunnar Allah ce ga waɗanda suka gabata a da; ba kuma za ka sami wani canji ba game da sunnar Allah

(1) Watau a tantance tsakaninsu da mata marasa kamun kai.

يَسْـَٔلُكَ ٱلنَّاسُ عَنِ ٱلسَّاعَةِ ۖ قُلْ إِنَّمَا عِلْمُهَا عِندَ ٱللَّهِ ۚ وَمَا يُدْرِيكَ
لَعَلَّ ٱلسَّاعَةَ تَكُونُ قَرِيبًا ﴿٦٣﴾ إِنَّ ٱللَّهَ لَعَنَ ٱلْكَٰفِرِينَ وَأَعَدَّ
لَهُمْ سَعِيرًا ﴿٦٤﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۖ لَّا يَجِدُونَ وَلِيًّا وَلَا نَصِيرًا
﴿٦٥﴾ يَوْمَ تُقَلَّبُ وُجُوهُهُمْ فِى ٱلنَّارِ يَقُولُونَ يَٰلَيْتَنَآ أَطَعْنَا ٱللَّهَ
وَأَطَعْنَا ٱلرَّسُولَا۠ ﴿٦٦﴾ وَقَالُوا۟ رَبَّنَآ إِنَّآ أَطَعْنَا سَادَتَنَا وَكُبَرَآءَنَا
فَأَضَلُّونَا ٱلسَّبِيلَا۠ ﴿٦٧﴾ رَبَّنَآ ءَاتِهِمْ ضِعْفَيْنِ مِنَ ٱلْعَذَابِ
وَٱلْعَنْهُمْ لَعْنًا كَبِيرًا ﴿٦٨﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَكُونُوا۟ كَٱلَّذِينَ
ءَاذَوْا۟ مُوسَىٰ فَبَرَّأَهُ ٱللَّهُ مِمَّا قَالُوا۟ ۚ وَكَانَ عِندَ ٱللَّهِ وَجِيهًا ﴿٦٩﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَقُولُوا۟ قَوْلًا سَدِيدًا ﴿٧٠﴾ يُصْلِحْ
لَكُمْ أَعْمَٰلَكُمْ وَيَغْفِرْ لَكُمْ ذُنُوبَكُمْ ۗ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ
فَقَدْ فَازَ فَوْزًا عَظِيمًا ﴿٧١﴾ إِنَّا عَرَضْنَا ٱلْأَمَانَةَ عَلَى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ وَٱلْجِبَالِ فَأَبَيْنَ أَن يَحْمِلْنَهَا وَأَشْفَقْنَ مِنْهَا وَحَمَلَهَا
ٱلْإِنسَٰنُ ۖ إِنَّهُۥ كَانَ ظَلُومًا جَهُولًا ﴿٧٢﴾ لِّيُعَذِّبَ ٱللَّهُ ٱلْمُنَٰفِقِينَ
وَٱلْمُنَٰفِقَٰتِ وَٱلْمُشْرِكِينَ وَٱلْمُشْرِكَٰتِ وَيَتُوبَ ٱللَّهُ
عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٧٣﴾

(63) Mutane suna tambayar ka game da (ranar) alƙiyama; ka ce (da su): “Saninta a wajen Allah kawai yake.” Ba ka sani ba ko watakila alƙiyamar za ta kasance kusa

(64) Lalle Allah Ya la’anci kafirai Ya kuma tanadar musu da (wutar) Sa’ira

(65) Masu dawwama ne a cikinta har abada; ba kuma za su sami wani majiɓinci ko mataimaki ba

(66) A ranar da za a riƙa jujjuya fuskokinsu cikin wuta, suna cewa: “Kaiconmu, ina ma da mun bi Allah mun bi Manzo!”

(67) Suka kuma ce: “Ya Ubangijinmu, lalle mu mun bi shugabanninmu da manyanmu sai suka ɓatar da mu hanya

(68) “Ya Ubangijinmu, Ka ba su azaba riɓi biyu, Ka kuma la’ance su babbar la’ana.”

(69)Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku zamanto kamar waɗanda suka cuci Musa sai Allah Ya wanke shi daga abin da suka faɗa (a kansa). Ya kuma kasance mai alfarma ne a wurin Allah

(70) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku faɗi Magana wadda take daidai ce

(71) Zai kyautata muku ayyukanku, Ya kuma gafarta muku zunubanku. Duk kuwa wanda ya bi Allah da Manzonsa, to haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma

(72) Lalle Mun bijiro da amana[1] ga sammai da ƙasa da duwatsu sai suka ƙi ɗaukar ta suka ji tsoron ta, sai kuwa mutum ya ɗauke ta; lalle shi (mutum) ya kasance mai zaluntar kansa ne, mai jahilci

(73) YDon Allah Ya azabtar da munafukai maza da munafukai mata, da mushirikai maza da mushirikai mata, Ya kuma karɓi tubar muminai maza da muminai mata. Allah kuwa Ya kasance Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(1) Amana a nan, su ne dokokin shari’a na umarni da hani.

Sura Saba'i

سُورَةُ سَبَإٍ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِى لَهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ وَلَهُ ٱلْحَمْدُ
فِى ٱلْءَاخِرَةِ ۚ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْخَبِيرُ ﴿١﴾ يَعْلَمُ مَا يَلِجُ فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا
يَخْرُجُ مِنْهَا وَمَا يَنزِلُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ وَمَا يَعْرُجُ فِيهَا ۚ وَهُوَ
ٱلرَّحِيمُ ٱلْغَفُورُ ﴿٢﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لَا تَأْتِينَا ٱلسَّاعَةُ ۖ
قُلْ بَلَىٰ وَرَبِّى لَتَأْتِيَنَّكُمْ عَٰلِمِ ٱلْغَيْبِ ۖ لَا يَعْزُبُ عَنْهُ مِثْقَالُ
ذَرَّةٍ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِى ٱلْأَرْضِ وَلَآ أَصْغَرُ مِن ذَٰلِكَ
وَلَآ أَكْبَرُ إِلَّا فِى كِتَٰبٍ مُّبِينٍ ﴿٣﴾ لِّيَجْزِىَ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُم مَّغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ
كَرِيمٌ ﴿٤﴾ وَٱلَّذِينَ سَعَوْ فِىٓ ءَايَٰتِنَا مُعَٰجِزِينَ أُو۟لَٰٓئِكَ
لَهُمْ عَذَابٌ مِّن رِّجْزٍ أَلِيمٌ ﴿٥﴾ وَيَرَى ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْعِلْمَ
ٱلَّذِىٓ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ هُوَ ٱلْحَقَّ وَيَهْدِىٓ إِلَىٰ صِرَٰطِ
ٱلْعَزِيزِ ٱلْحَمِيدِ ﴿٦﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ هَلْ نَدُلُّكُمْ عَلَىٰ رَجُلٍ
يُنَبِّئُكُمْ إِذَا مُزِّقْتُمْ كُلَّ مُمَزَّقٍ ۙ إِنَّكُمْ لَفِى خَلْقٍ جَدِيدٍ ﴿٧﴾

(1) Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Wanda duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nasa ne, kuma godiya ta tabbata a gare Shi a lahira. Shi kuwa Mai hikima ne, Masani

(2) Yana sane da abin da yake shiga cikin ƙasa da abin da yake fitowa daga cikinta, da kuma abin da yake sauka daga sama da abin da yake hawa cikinta. Kuma Shi Mai rahama ne, Mai gafara

(3) Kuma waɗanda suka kafirta suka ce: "Ranar alƙiyama ba za ta zo mana ba." Ka ce: "A'a, na rantse da Ubangijina, tabbas za ta zo muku, (Allah) Shi ne Masanin gaibu; ba abin da yake ɓoye a gare Shi; daidai da ƙwayar zarra a cikin sammai ko a ƙasa, ko wanda ya fi wannan ƙanƙanta ko ya fi girma, face yana nan (a rubuce) a cikin Lauhul-Mahafuzu

(4) "Don Ya saka wa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka kyawawa. Waɗannan suna da gafara da arziki na karamci."

(5) Waɗanda kuwa suka yi ɓarna a cikin ayoyinmu don su nuna gazawarmu[1], waɗannan suna da mummunar azaba mai raɗaɗi

(6) Waɗanda aka bai wa ilimi kuma suna ganin abin da aka saukar maka daga Ubangijinka shi ne gaskiya, kuma yana shiryarwa ne zuwa hanyar (Allah) Mabuwayi, Sha-yabo

(7) Waɗanda suka kafirta suka ce: "Shin ma nuna muku wani mutum da zai ba ku labarin cewa, idan an yayyaga ku yugu-yugu lallai za ku dawo cikin wata halitta sabuwa?

(1) Watau suna sukar ayoyin Allah da cewa sihiri ne ko bokanci ko waqa.

أَفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَم بِهِۦ جِنَّةُۢۗ بَلِ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ
فِي ٱلۡعَذَابِ وَٱلضَّلَٰلِ ٱلۡبَعِيدِ ﴿٨﴾ أَفَلَمۡ يَرَوۡاْ إِلَىٰ مَا بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ
وَمَا خَلۡفَهُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِۚ إِن نَّشَأۡ نَخۡسِفۡ بِهِمُ ٱلۡأَرۡضَ
أَوۡ نُسۡقِطۡ عَلَيۡهِمۡ كِسَفٗا مِّنَ ٱلسَّمَآءِۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ
لِّكُلِّ عَبۡدٖ مُّنِيبٖ ﴿٩﴾ ۞ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا دَاوُۥدَ مِنَّا فَضۡلٗاۖ
يَٰجِبَالُ أَوِّبِي مَعَهُۥ وَٱلطَّيۡرَۖ وَأَلَنَّا لَهُ ٱلۡحَدِيدَ ﴿١٠﴾ أَنِ ٱعۡمَلۡ
سَٰبِغَٰتٖ وَقَدِّرۡ فِي ٱلسَّرۡدِۖ وَٱعۡمَلُواْ صَٰلِحًاۖ إِنِّي بِمَا تَعۡمَلُونَ
بَصِيرٞ ﴿١١﴾ وَلِسُلَيۡمَٰنَ ٱلرِّيحَ غُدُوُّهَا شَهۡرٞ وَرَوَاحُهَا شَهۡرٞۖ
وَأَسَلۡنَا لَهُۥ عَيۡنَ ٱلۡقِطۡرِۖ وَمِنَ ٱلۡجِنِّ مَن يَعۡمَلُ بَيۡنَ يَدَيۡهِ بِإِذۡنِ
رَبِّهِۦۖ وَمَن يَزِغۡ مِنۡهُمۡ عَنۡ أَمۡرِنَا نُذِقۡهُ مِنۡ عَذَابِ ٱلسَّعِيرِ ﴿١٢﴾
يَعۡمَلُونَ لَهُۥ مَا يَشَآءُ مِن مَّحَٰرِيبَ وَتَمَٰثِيلَ وَجِفَانٖ كَٱلۡجَوَابِ
وَقُدُورٖ رَّاسِيَٰتٍۚ ٱعۡمَلُوٓاْ ءَالَ دَاوُۥدَ شُكۡرٗاۚ وَقَلِيلٞ مِّنۡ عِبَادِيَ
ٱلشَّكُورُ ﴿١٣﴾ فَلَمَّا قَضَيۡنَا عَلَيۡهِ ٱلۡمَوۡتَ مَا دَلَّهُمۡ عَلَىٰ مَوۡتِهِۦٓ
إِلَّا دَآبَّةُ ٱلۡأَرۡضِ تَأۡكُلُ مِنسَأَتَهُۥۖ فَلَمَّا خَرَّ تَبَيَّنَتِ ٱلۡجِنُّ
أَن لَّوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ٱلۡغَيۡبَ مَا لَبِثُواْ فِي ٱلۡعَذَابِ ٱلۡمُهِينِ ﴿١٤﴾

(8) "Shin ya yi wa Allah ƙarya ne, ko kuma yana da wani taɓin hankali ne?" Ba haka ba ne, waɗanda ba sa yin imani da lahira suna cikin azaba da ɓata mai nisa

(9) Ba sa dubawa su ga abin da yake gabansu da abin da yake bayansu na sama da ƙasa? In da Mun ga dama sai Mu nutsar da su cikin ƙasa ko kuma Mu rufto musu da wani yanki daga sama. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya ga duk wani bawa mai komawa ga Allah

(10) Kuma haƙiƙa Mun bai wa Dawuda falala daga gare Mu; cewa: "Ya ku duwatsu ku riƙa amsa tasbihi tare da shi," da kuma tsuntsaye; Muka kuma tausasa masa ƙarfe

(11) (Muka ce da shi): "Ka riƙa yin cikakken silke, kuma ka kintata wajen yin saƙar; kuma (kai Dawuda da iyalinka) ku yi ayyuka nagari; lalle Ni Mai ganin abin da kuke aikatawa ne."

(12) Kuma (Muka hore wa) Sulaimanu iska, tafiyarta ta safe wata guda ce, ta yamma ma kuma wata guda ce; Muka kuma ɓuɓɓugo masa da narkakkiyar tagulla tana gudana. Daga aljannu kuma akwai masu aiki a wajensa da umarnin Ubangijinsa; wanda kuwa ya kauce wa umarninmu daga cikinsu, to za Mu ɗanɗana masa azabar wutar Sa'ira

(13) Suna aikata masa abubuwan da yake bukata na manya-manyan gine-gine[1] da mutum-mutumi[2] da akusa manya-manya kamar tafkuna da kafaffun tukwane. Ya ku iyalin Dawuda, ku yi aikin (ɗa'a) domin godiya. Masu godiya daga bayina kuwa kaɗan ne

(14) Sannan lokacin da Muka ƙaddara masa mutuwa ba abin da ya nuna musu mutuwarsa sai gara da ta riƙa cin sandarsa[3]; to lokacin da ya faɗi sai aljannu suka gane cewa da sun san gaibu da ba su zauna cikin azabar wulaƙanci ba

(1) Watau wuraren ibada.

(2) A wancan lokacin ba a haramta yin su ba. Sai bayan zuwan Annabi ( ) ne ya haramta surantasu ko gina su.

(3) Sandarsa da yake tsaye a kanta.

لَقَدْ كَانَ لِسَبَإٍ فِي مَسْكَنِهِمْ ءَايَةٌ ۖ جَنَّتَانِ عَن يَمِينٍ وَشِمَالٍ ۖ
كُلُوا۟ مِن رِّزْقِ رَبِّكُمْ وَٱشْكُرُوا۟ لَهُۥ ۚ بَلْدَةٌ طَيِّبَةٌ وَرَبٌّ غَفُورٌ
﴿١٥﴾ فَأَعْرَضُوا۟ فَأَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ سَيْلَ ٱلْعَرِمِ وَبَدَّلْنَٰهُم بِجَنَّتَيْهِمْ
جَنَّتَيْنِ ذَوَاتَىْ أُكُلٍ خَمْطٍ وَأَثْلٍ وَشَىْءٍ مِّن سِدْرٍ قَلِيلٍ
﴿١٦﴾ ذَٰلِكَ جَزَيْنَٰهُم بِمَا كَفَرُوا۟ ۖ وَهَلْ نُجَٰزِىٓ إِلَّا ٱلْكَفُورَ ﴿١٧﴾
وَجَعَلْنَا بَيْنَهُمْ وَبَيْنَ ٱلْقُرَى ٱلَّتِى بَٰرَكْنَا فِيهَا قُرًى ظَٰهِرَةً
وَقَدَّرْنَا فِيهَا ٱلسَّيْرَ ۖ سِيرُوا۟ فِيهَا لَيَالِىَ وَأَيَّامًا ءَامِنِينَ ﴿١٨﴾
فَقَالُوا۟ رَبَّنَا بَٰعِدْ بَيْنَ أَسْفَارِنَا وَظَلَمُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ فَجَعَلْنَٰهُمْ
أَحَادِيثَ وَمَزَّقْنَٰهُمْ كُلَّ مُمَزَّقٍ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّكُلِّ صَبَّارٍ
شَكُورٍ ﴿١٩﴾ وَلَقَدْ صَدَّقَ عَلَيْهِمْ إِبْلِيسُ ظَنَّهُۥ فَٱتَّبَعُوهُ إِلَّا
فَرِيقًا مِّنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٢٠﴾ وَمَا كَانَ لَهُۥ عَلَيْهِم مِّن سُلْطَٰنٍ
إِلَّا لِنَعْلَمَ مَن يُؤْمِنُ بِٱلْءَاخِرَةِ مِمَّنْ هُوَ مِنْهَا فِى شَكٍّ ۗ
وَرَبُّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ حَفِيظٌ ﴿٢١﴾ قُلِ ٱدْعُوا۟ ٱلَّذِينَ زَعَمْتُم مِّن
دُونِ ٱللَّهِ لَا يَمْلِكُونَ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِى
ٱلْأَرْضِ وَمَا لَهُمْ فِيهِمَا مِن شِرْكٍ وَمَا لَهُۥ مِنْهُم مِّن ظَهِيرٍ ﴿٢٢﴾

(15) Hakika akwai aya game da gidajen kabilar Saba'u (ta kasar Yaman); ita ce gonakai guda biyu na lambu a hagu da dama; (aka ce da su): "Ku ci daga arzikin Ubangijinku, kuma ku gode masa. Kasa ce mai dadin zama da kuma Ubangiji mai gafara

(16) Sai suka bijire, sai Muka aiko musu da ambaliyar madatsar ruwan Arimu, Muka kuma musanya musu gonakin nan nasu biyu da wasu gonakin biyu ma'abota 'ya'ya masu daci da kuma itacen tsamiya, da wani abu kadan na 'ya'yan magarya

(17) Wannan shi ne Muka saka musu (da shi) saboda kafircinsu; ba kuwa Ma yin sakamako (irin wannan) sai ga mai butulci

(18) Muka kuma sanya wasu alkaryu mabayyana a tsakaninsu (mutan Saba'u) da alkaryar da Muka sa albarka a cikinta (wato kasar Sham)[1], Muka kuma takaita zangon tafiya a tsakaninsu (alkaryun; Muka ce): "Ku yi tafiya a cikinsu dare da rana cikin aminci."

(19) Sai suka ce: "Ya Ubangijinmu, Ka kaddara nisa tsakanin zangunan tafiyarmu," suka kuwa zalunci kansu, sai Muka mai da su tarihi[2], Muka kuma warwatsa su wuri-wuri. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga duk wani mai yin hakuri, mai yin godiya

(20) Kuma hakika Iblisu ya tabbatar da zatonsa a kansu gaskiya ne[3], sai suka bi shi, in ban da wata kungiya ta muminai

(21) Shi kuwa ba shi da wani karfi a kansu, sai dai (Mun yi haka ne) don Mu bayyana wanda yake imani da ranar lahira da kuma wanda yake cikin shakka game da ita. Ubangijinka kuwa Mai kiyaye komai ne

(22) Ka ce: "Ku kirawo wadanda kuka riya (cewa su ne iyayen giji) ba Allah ba;" ba sa mallakar wani abu daidai da kwayar zarra a cikin sammai ko a cikin kasa, ba kuma su da wata tarayya a cikinsu, ba Shi kuma da wani mataimaki daga cikinsu

(1) Watau Allah ( ) ya sanya wasu fitattun alqaryu da matafiya kan iya hango su daga nesa, wanda hakan ya sauqaqa musu tafiye-tafiyensu.

(2) Watau Allah ( ) ya tarwatsa su suka warwatsu a garuruwa daban-daban har haxuwa da junansu ta yi musu wahala.

(3) Watau na cewa zai iya vatar da su ya raba su da gaskiya.

وَلَا تَنفَعُ ٱلشَّفَٰعَةُ عِندَهُۥٓ إِلَّا لِمَنْ أَذِنَ لَهُۥ ۚ حَتَّىٰٓ إِذَا فُزِّعَ عَن
قُلُوبِهِمْ قَالُوا۟ مَاذَا قَالَ رَبُّكُمْ ۖ قَالُوا۟ ٱلْحَقَّ ۖ وَهُوَ ٱلْعَلِىُّ ٱلْكَبِيرُ
﴿٢٣﴾ ۞ قُلْ مَن يَرْزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ قُلِ ٱللَّهُ ۖ
وَإِنَّآ أَوْ إِيَّاكُمْ لَعَلَىٰ هُدًى أَوْ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٢٤﴾ قُل
لَّا تُسْـَٔلُونَ عَمَّآ أَجْرَمْنَا وَلَا نُسْـَٔلُ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿٢٥﴾ قُلْ
يَجْمَعُ بَيْنَنَا رَبُّنَا ثُمَّ يَفْتَحُ بَيْنَنَا بِٱلْحَقِّ وَهُوَ ٱلْفَتَّاحُ ٱلْعَلِيمُ
﴿٢٦﴾ قُلْ أَرُونِىَ ٱلَّذِينَ أَلْحَقْتُم بِهِۦ شُرَكَآءَ ۖ كَلَّا ۚ بَلْ هُوَ ٱللَّهُ
ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٢٧﴾ وَمَآ أَرْسَلْنَٰكَ إِلَّا كَآفَّةً لِّلنَّاسِ
بَشِيرًا وَنَذِيرًا وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٢٨﴾
وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلْوَعْدُ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٢٩﴾
قُل لَّكُم مِّيعَادُ يَوْمٍ لَّا تَسْتَـْٔخِرُونَ عَنْهُ سَاعَةً وَلَا تَسْتَقْدِمُونَ
﴿٣٠﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لَن نُّؤْمِنَ بِهَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ وَلَا
بِٱلَّذِى بَيْنَ يَدَيْهِ ۗ وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلظَّٰلِمُونَ مَوْقُوفُونَ عِندَ
رَبِّهِمْ يَرْجِعُ بَعْضُهُمْ إِلَىٰ بَعْضٍ ٱلْقَوْلَ يَقُولُ ٱلَّذِينَ
ٱسْتُضْعِفُوا۟ لِلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُوا۟ لَوْلَآ أَنتُمْ لَكُنَّا مُؤْمِنِينَ ﴿٣١﴾

(23) Kuma ceto ba ya amfani a wurinsa sai ga wanda Ya yi wa izinin yin sa. Har idan an cire tsoro daga cikin zukatansu[1], sai su ce: "Me Ubangijinku Ya ce ne?" Suka ce: "Gaskiya Ya faɗa, kuma Shi ne Maɗaukaki, Mai girma."

(24) Ka ce: "Wane ne yake arzuta ku daga sammai da ƙasa?" Ka ce: "Allah ne; kuma mu ko ku (ɗaya daga cikinmu) lalle yana a kan shiriya ko kuma yana cikin ɓata mabayyani."

(25) Ka ce: "Ba za a tambaye ku ba game da laifin da muka yi, mu ma kuma ba za a tambaye mu ba game da abin da kuke aikatawa."

(26) Ka ce: "Ubangijinmu zai tattara mu sannan Ya yi hukunci a tsakaninmu da gaskiya, Shi ne kuwa Mai hukunci, Masani."

(27) Ka ce: "Ku nuna min waɗanda kuka riskar da su a matsayin abokan tarayya da Shi; ku bar wannan magana! Shi ne Allah Mabuwayi Mai hikima."

(28) Ba Mu kuma aiko ka ba sai ga mutane baki ɗaya kana mai albishir mai kuma gargaɗi, sai dai kuma yawancin mutane ba sa sanin (hakan)

(29) Suna kuma cewa: "Yaushe ne wannan alƙawarin (na ranar alƙiyama) zai zo, idan kun kasance masu gaskiya?"

(30) Ka ce: "Kuna da ajiyayyar rana da ba za ku jinkirta ba daga gare ta daidai da sa'a, ba kuma za ku wuce ta ba."

(31) Kuma kafirai suka ce: "Ba za mu yi imani da wannan Alƙur'ani ba, haka ma da wanda yake gabaninsa (na saukakkun littattafai)." Da kuwa za ka ga lokacin da za a tsai da azzalumai wajen Ubangijinsu suna mayar wa da juna magana, masu rauninsu (mabiya) suna ce wa masu girman kai (watau shugabanninsu): "Ba don ku ba da mun zamanto muminai."

(1) Saboda cikar mulkin Allah idan ya yi wata magana mala'iku gaba xaya sukan buga fukafukansu suna masu rusunawa ga maganarsa, suna masu cike da tsoro.

قَالَ ٱلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُوا۟ لِلَّذِينَ ٱسْتُضْعِفُوٓا۟ أَنَحْنُ صَدَدْنَٰكُمْ
عَنِ ٱلْهُدَىٰ بَعْدَ إِذْ جَآءَكُم بَلْ كُنتُم مُّجْرِمِينَ ﴿٣٢﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ
ٱسْتُضْعِفُوا۟ لِلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُوا۟ بَلْ مَكْرُ ٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ إِذْ
تَأْمُرُونَنَآ أَن نَّكْفُرَ بِٱللَّهِ وَنَجْعَلَ لَهُۥٓ أَندَادًا ۚ وَأَسَرُّوا۟ ٱلنَّدَامَةَ
لَمَّا رَأَوُا۟ ٱلْعَذَابَ ۚ وَجَعَلْنَا ٱلْأَغْلَٰلَ فِىٓ أَعْنَاقِ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ۖ
هَلْ يُجْزَوْنَ إِلَّا مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٣٣﴾ وَمَآ أَرْسَلْنَا فِى قَرْيَةٍ
مِّن نَّذِيرٍ إِلَّا قَالَ مُتْرَفُوهَآ إِنَّا بِمَآ أُرْسِلْتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ ﴿٣٤﴾
وَقَالُوا۟ نَحْنُ أَكْثَرُ أَمْوَٰلًا وَأَوْلَٰدًا وَمَا نَحْنُ بِمُعَذَّبِينَ ﴿٣٥﴾
قُلْ إِنَّ رَبِّى يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقْدِرُ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ
ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٣٦﴾ وَمَآ أَمْوَٰلُكُمْ وَلَآ أَوْلَٰدُكُم بِٱلَّتِى تُقَرِّبُكُمْ
عِندَنَا زُلْفَىٰٓ إِلَّا مَنْ ءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَأُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ جَزَآءُ
ٱلضِّعْفِ بِمَا عَمِلُوا۟ وَهُمْ فِى ٱلْغُرُفَٰتِ ءَامِنُونَ ﴿٣٧﴾ وَٱلَّذِينَ
يَسْعَوْنَ فِىٓ ءَايَٰتِنَا مُعَٰجِزِينَ أُو۟لَٰٓئِكَ فِى ٱلْعَذَابِ مُحْضَرُونَ ﴿٣٨﴾
قُلْ إِنَّ رَبِّى يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ وَيَقْدِرُ لَهُۥ ۚ
وَمَآ أَنفَقْتُم مِّن شَىْءٍ فَهُوَ يُخْلِفُهُۥ ۖ وَهُوَ خَيْرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ﴿٣٩﴾

(32) Masu girman kan suka ce wa raunanan: "Yanzu mu muka hana ku ku shiriya bayan ta zo muku? Ba haka ba ne, kun dai kasance masu laifi ne."

(33) Raunanan kuma suka ce da manyan masu girman kan: "Ba haka ba ne, makircin dare da na rana ne (da kuke ƙulla mana ya hana mu shiriya), yayin da kuke umartar mu da mu kafirce wa Allah, mu kuma sanya masa abokan tarayya." Suka kuma bayyana nadama lokacin da suka ga azaba, kuma Muka sanya ƙuƙumi a wuyan waɗanda suka kafirta, ba kuwa za a saka musu da komai ba sai da irin abin da suka kasance suna aikatawa

(34) Ba Mu taɓa aiko wani mai gargaɗi cikin wata alƙarya ba sai mawadatan cikinta sun ce: "Mu dai masu kafirce wa abin da aka aiko ku da shi ne."

(35) Suka kuma ce: "Mu muka fi kowa yawan dukiya da 'ya'ya, kuma mu ba waɗanda za a azabtar ba ne."

(36) Ka ce: "Lalle Ubangijina Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, Ya kuma ƙuntata, sai dai kuma yawancin mutane ba su san (haka) ba."

(37) Kuma ba dukiyoyinku da 'ya'yanku ne za su kusantar da ku gare Mu ba, sai wanda ya yi imani ya kuma yi aiki nagari, to waɗannan suna da sakamako ninkin-baninki saboda abin da suka aikata, suna kuma amintattu cikin benaye

(38) Waɗanda kuwa suke yin ƙoƙari na ɓata ayoyinmu, don su nuna gazawarmu, waɗannan cikin azaba za a halartar da su

(39) Ka ce: "Lalle Ubangijna Yana shimfiɗa arziki ga wanda ya ga dama cikin bayinsa, Yana kuma ƙuntata masa. Kuma duk abin da kuka ciyar (don Allah), to Shi ne zai ba ku madadinsa, Shi ne kuwa Fiyayyen masu arzutawa."

وَيَوْمَ يَحْشُرُهُمْ جَمِيعًا ثُمَّ يَقُولُ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ أَهَٰٓؤُلَآءِ إِيَّاكُمْ كَانُوا۟
يَعْبُدُونَ ﴿٤٠﴾ قَالُوا۟ سُبْحَٰنَكَ أَنتَ وَلِيُّنَا مِن دُونِهِم ۖ بَلْ كَانُوا۟
يَعْبُدُونَ ٱلْجِنَّ ۖ أَكْثَرُهُم بِهِم مُّؤْمِنُونَ ﴿٤١﴾ فَٱلْيَوْمَ لَا يَمْلِكُ
بَعْضُكُمْ لِبَعْضٍ نَّفْعًا وَلَا ضَرًّا وَنَقُولُ لِلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ ذُوقُوا۟ عَذَابَ
ٱلنَّارِ ٱلَّتِى كُنتُم بِهَا تُكَذِّبُونَ ﴿٤٢﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٍ
قَالُوا۟ مَا هَٰذَآ إِلَّا رَجُلٌ يُرِيدُ أَن يَصُدَّكُمْ عَمَّا كَانَ يَعْبُدُ ءَابَآؤُكُمْ
وَقَالُوا۟ مَا هَٰذَآ إِلَّآ إِفْكٌ مُّفْتَرًى ۚ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لِلْحَقِّ لَمَّا
جَآءَهُمْ إِنْ هَٰذَآ إِلَّا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿٤٣﴾ وَمَآ ءَاتَيْنَٰهُم مِّن كُتُبٍ
يَدْرُسُونَهَا ۖ وَمَآ أَرْسَلْنَآ إِلَيْهِمْ قَبْلَكَ مِن نَّذِيرٍ ﴿٤٤﴾ وَكَذَّبَ
ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ وَمَا بَلَغُوا۟ مِعْشَارَ مَآ ءَاتَيْنَٰهُمْ فَكَذَّبُوا۟
رُسُلِى ۖ فَكَيْفَ كَانَ نَكِيرِ ﴿٤٥﴾ ۞ قُلْ إِنَّمَآ أَعِظُكُم بِوَٰحِدَةٍ ۖ أَن
تَقُومُوا۟ لِلَّهِ مَثْنَىٰ وَفُرَٰدَىٰ ثُمَّ تَتَفَكَّرُوا۟ ۚ مَا بِصَاحِبِكُم مِّن
جِنَّةٍ ۚ إِنْ هُوَ إِلَّا نَذِيرٌ لَّكُم بَيْنَ يَدَىْ عَذَابٍ شَدِيدٍ ﴿٤٦﴾ قُلْ
مَا سَأَلْتُكُم مِّنْ أَجْرٍ فَهُوَ لَكُمْ ۖ إِنْ أَجْرِىَ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ ۖ وَهُوَ عَلَىٰ
كُلِّ شَىْءٍ شَهِيدٌ ﴿٤٧﴾ قُلْ إِنَّ رَبِّى يَقْذِفُ بِٱلْحَقِّ عَلَّٰمُ ٱلْغُيُوبِ ﴿٤٨﴾

(40) Kuma (ka tuna) ranar da zai tattaro su gaba ɗaya sannan Ya ce da mala'iku: "Ashe yanzu ku ne waɗannan suka kasance suna bauta wa?"
(41) Suka ce: "Tsarki ya tabbata a gare Ka, Kai ne Majiɓincinmu ba su ba." Ba haka ba ne, sun kasance suna bauta wa aljannu ne; mafiya yawansu masu yin imani da su ne
(42) (Sai Allah Ya ce): "To yau shashinku ba zai mallaki amfani ga wani sashi ba ko cutarwa," za kuma Mu ce da waɗanda suka kafirta: "Ku ɗanɗani azabar wutar da kuka kasance kuna ƙaryata ta."
(43) Idan kuma ana karanta musu ayoyinmu mabayyana sai su ce: "Wannan ai ba wani ba ne sai wani mutum da yake nufin ya hana ku (bauta wa) abin da iyayenku suka kasance suna bauta wa." Suka kuma ce: "Wannan ai ba wani abu ba ne in ban da ƙarya da aka ƙirƙira." Waɗanda kuma suka kafirta suka ce game da gaskiya yayin da ta zo musu: "Wannan ba wani abu ba ne sai sihiri mabayyani."
(44) Kuma ba Mu kawo musu wasu littattafai da suke karantawa ba, kuma ba Mu aiko musu da wani mai gargaɗi ba gabaninka
(45) Kuma waɗanda suka gabace su sun ƙaryata (annabawa; kafiran Makka) kuwa ba su kai ushurin abin da Muka ba su ba, to su ma sun ƙaryata manzannina; to yaya tsawatarwata ta kasance (gare su)?
(46) Ka ce: "Ni dai kawai ina yi muku wa'azi ne da abu ɗaya; cewa ku tsaya don Allah; bibbiyu da kuma ɗai-ɗai, sannan ku yi tunani. Ba wata hauka tare da mutuminku, shi ba wani ne ba, sai mai yi muku gargaɗin azaba mai tsanani da take gabanku."
(47) Ka ce: "Abin da na tambaye ku na wani lada to naku ne[1]; ladana yana wajen Allah kawai; kuma Shi Mai shaida ne a kan komai."

(1) Watau ko da kuwa a ce ya nemi su bayar da wani lada a kan hakan, to ladan nasu ne, ba nasa ba ne, shi sakamakonsa yana wajen Allah shi kaxai.

قُلْ جَآءَ ٱلْحَقُّ وَمَا يُبْدِئُ ٱلْبَٰطِلُ وَمَا يُعِيدُ ﴿٤٩﴾ قُلْ إِن ضَلَلْتُ
فَإِنَّمَآ أَضِلُّ عَلَىٰ نَفْسِى ۖ وَإِنِ ٱهْتَدَيْتُ فَبِمَا يُوحِىٓ إِلَىَّ رَبِّىٓ ۚ إِنَّهُۥ
سَمِيعٌ قَرِيبٌ ﴿٥٠﴾ وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذْ فَزِعُوا۟ فَلَا فَوْتَ وَأُخِذُوا۟ مِن
مَّكَانٍ قَرِيبٍ ﴿٥١﴾ وَقَالُوٓا۟ ءَامَنَّا بِهِۦ ۖ وَأَنَّىٰ لَهُمُ ٱلتَّنَاوُشُ مِن
مَّكَانٍۭ بَعِيدٍ ﴿٥٢﴾ وَقَدْ كَفَرُوا۟ بِهِۦ مِن قَبْلُ ۖ وَيَقْذِفُونَ
بِٱلْغَيْبِ مِن مَّكَانٍۭ بَعِيدٍ ﴿٥٣﴾ وَحِيلَ بَيْنَهُمْ وَبَيْنَ مَا يَشْتَهُونَ
كَمَا فُعِلَ بِأَشْيَاعِهِم مِّن قَبْلُ ۚ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ فِى شَكٍّ مُّرِيبٍ ﴿٥٤﴾

سُورَةُ فَاطِرٍ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ جَاعِلِ ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلًا أُو۟لِىٓ
أَجْنِحَةٍ مَّثْنَىٰ وَثُلَٰثَ وَرُبَٰعَ ۚ يَزِيدُ فِى ٱلْخَلْقِ مَا يَشَآءُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ
كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿١﴾ مَّا يَفْتَحِ ٱللَّهُ لِلنَّاسِ مِن رَّحْمَةٍ فَلَا مُمْسِكَ لَهَا ۖ
وَمَا يُمْسِكْ فَلَا مُرْسِلَ لَهُۥ مِنۢ بَعْدِهِۦ ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٢﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱذْكُرُوا۟ نِعْمَتَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ ۚ هَلْ مِنْ خَٰلِقٍ غَيْرُ ٱللَّهِ
يَرْزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ ۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ فَأَنَّىٰ تُؤْفَكُونَ ﴿٣﴾



(49) Ka ce: “Gaskiya ta zo ƙarya kuma ba za ta sake faruwa ba, ba kuma za ta dawo ba.”
(50) Ka ce: “Idan na ɓata to na ɓata ne a kan kaina; idan kuwa na shiriya to (na shiriya ne) da abin da Ubangijina Yake yi min wahayinsa. Lalle Shi Mai ji ne, Makusanci.”
(51) Da kuwa za ka ga sanda (kafirai) za su firgita, (da ganin azaba), sannan ba wata makuɓuta, kuma aka damƙo su daga makusancin wuri
(52) Suka kuma ce: “Mun yi imani da shi,” yaya kuwa za su iya kamo (wannan imani) daga wuri mai nisa (wato duniya)?
(53) Alhalin kuma haƙiƙa sun riga sun kafirta da shi a da can, kuma suna jifa (da zato) ta wani wuri mai nisa[1]
(54) Aka kuma kange tsakaninsu da abin da suke sha’awa (na jin dadin rayuwa ko komawa duniya) kamar yadda aka yi da ire-irensu tun da can. Lalle su sun kasance cikin shakka mai cike da kokwanto

Sura Fadir

(1) Dukkan yabo ya tabbata ga Allah, Mahaliccin sammai da ƙasa Mai sanya mala’iku manzanni masu fukafukai bibbiyu da masu uku-uku da kuma masu huɗu-huɗu. Yakan kuma ƙara abin da Ya ga dama ga halittar[2]. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai
(2) Abin da Allah Yake yi wa mutane buɗi da shi na rahama ba mai iya riƙe shi; abin da kuma Yake riƙewa ba mai iya sakin sa bayansa. Shi kuma Mabuwayi ne, Mai hikima
(3) Ya ku mutane, ku tuna ni’imar Allah a gare ku. Yanzu akwai wani mahalicci ban da Allah wanda zai arzuta ku daga sama da ƙasa? Babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. To ta yaya ake karkatar da ku?

(1) Watau sun riqa jifan Manzon Allah ( ) da zace-zace iri-iri da shaci-faxi, wani lokaci su kira shi mai sihiri, wani lokaci su ce masa boka, ko su kira shi mawaqi.

(2) Don haka akwai mala’iku masu fukafukai fiye da huxu, ya kuma qara wa wanda ya ga dama kyau ko wata gava.

وَإِن يُكَذِّبُوكَ فَقَدْ كُذِّبَتْ رُسُلٌ مِّن قَبْلِكَ ۚ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرْجَعُ ٱلْأُمُورُ
٤ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ ۖ فَلَا تَغُرَّنَّكُمُ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا
وَلَا يَغُرَّنَّكُم بِٱللَّهِ ٱلْغَرُورُ ٥ إِنَّ ٱلشَّيْطَٰنَ لَكُمْ عَدُوٌّ فَٱتَّخِذُوهُ
عَدُوًّا ۚ إِنَّمَا يَدْعُوا۟ حِزْبَهُۥ لِيَكُونُوا۟ مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلسَّعِيرِ ٦ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ لَهُمْ عَذَابٌ شَدِيدٌ ۖ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُم
مَّغْفِرَةٌ وَأَجْرٌ كَبِيرٌ ٧ أَفَمَن زُيِّنَ لَهُۥ سُوٓءُ عَمَلِهِۦ فَرَءَاهُ حَسَنًا ۖ فَإِنَّ
ٱللَّهَ يُضِلُّ مَن يَشَآءُ وَيَهْدِى مَن يَشَآءُ ۖ فَلَا تَذْهَبْ نَفْسُكَ عَلَيْهِمْ
حَسَرَٰتٍ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِمَا يَصْنَعُونَ ٨ وَٱللَّهُ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ
ٱلرِّيَٰحَ فَتُثِيرُ سَحَابًا فَسُقْنَٰهُ إِلَىٰ بَلَدٍ مَّيِّتٍ فَأَحْيَيْنَا بِهِ ٱلْأَرْضَ
بَعْدَ مَوْتِهَا ۚ كَذَٰلِكَ ٱلنُّشُورُ ٩ مَن كَانَ يُرِيدُ ٱلْعِزَّةَ فَلِلَّهِ ٱلْعِزَّةُ جَمِيعًا ۚ
إِلَيْهِ يَصْعَدُ ٱلْكَلِمُ ٱلطَّيِّبُ وَٱلْعَمَلُ ٱلصَّٰلِحُ يَرْفَعُهُۥ ۚ وَٱلَّذِينَ
يَمْكُرُونَ ٱلسَّيِّـَٔاتِ لَهُمْ عَذَابٌ شَدِيدٌ ۖ وَمَكْرُ أُو۟لَٰٓئِكَ هُوَ يَبُورُ
١٠ وَٱللَّهُ خَلَقَكُم مِّن تُرَابٍ ثُمَّ مِن نُّطْفَةٍ ثُمَّ جَعَلَكُمْ أَزْوَٰجًا ۚ
وَمَا تَحْمِلُ مِنْ أُنثَىٰ وَلَا تَضَعُ إِلَّا بِعِلْمِهِۦ ۚ وَمَا يُعَمَّرُ مِن مُّعَمَّرٍ
وَلَا يُنقَصُ مِنْ عُمُرِهِۦٓ إِلَّا فِى كِتَٰبٍ ۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ ١١

(4) Idan kuwa suka ƙaryata ka to haƙiƙa an ƙaryata wasu manzannin a gabaninka. Zuwa ga Allah ne kaɗai ake mayar da al'amura

(5) Ya ku mutane, lalle alƙawarin Allah gaskiya ne, saboda haka kada rayuwar duniya ta ruɗe ku; kada kuma mai ruɗarwa (Shaiɗan) ya ruɗe ku game da Allah

(6) Lalle Shaiɗan maƙiyinku ne, saboda haka sai ku riƙe shi maƙiyi. Lalle yana kiran mutanensa ne don su zama 'yan wuta

(7) Waɗanda suka kafirta suna da (sakamakon) azaba mai tsanani; waɗanda kuwa suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, to suna da gafara da lada mai girma

(8) Yanzu wanda aka ƙawata wa mummunan aikinsa ya gan shi kyakkyawa (zai yi daidai da wanda Allah Ya shiryar)? To lalle Allah Yana ɓatar da wanda Ya ga dama Ya shiryi wanda Ya ga dama; saboda haka kada ka halakar da kanka don baƙin ciki game da su. Lalle Allah Masanin abin da suke aikatawa ne

(9) Kuma Allah Shi ne wanda ya aiko da iska sai ta motsa hadari, sai Muka koro shi zuwa ga mataccen gari, sai Muka raya ƙasa da shi bayan mutuwarta. Kamar haka tayar da (matattu) yake

(10) Wanda ya zamanto yana nufin ɗaukaka, to ɗaukaka gaba ɗayanta ta Allah ce. Daɗaɗan kalmomi[1] zuwa wurinsa suke hawa, kyakkyawan aiki kuwa shi yake ɗaukaka shi. Waɗanda kuwa suke shirya makirci suna da (sakamakon) azaba mai tsanani, kuma makircin waɗannan shi ne yake lalacewa

(11) Kuma Allah Ya halicce ku ne daga turɓaya sannan daga maniyyi, sannan kuma Ya mayar da ku maza da mata. Kuma mace ba za ta ɗauki ciki ba, ba kuma za ta haifu ba sai da saninsa. Ba kuma wani mai tsawon rai da za a raya shi, ko kuma wani da za a rage tsawon ransa face yana (rubuce) a cikin Lauhul-Mahafuzu. Wannan kuwa a wurin Allah mai sauƙi ne

(1) Watau kamar kalmar shahada da karatun Alqur'ani da ambaton Allah.

وَمَا يَسْتَوِي ٱلْبَحْرَانِ هَٰذَا عَذْبٌ فُرَاتٌ سَآئِغٌ شَرَابُهُۥ وَهَٰذَا
مِلْحٌ أُجَاجٌ ۖ وَمِن كُلٍّ تَأْكُلُونَ لَحْمًا طَرِيًّا وَتَسْتَخْرِجُونَ
حِلْيَةً تَلْبَسُونَهَا ۖ وَتَرَى ٱلْفُلْكَ فِيهِ مَوَاخِرَ لِتَبْتَغُوا۟ مِن فَضْلِهِۦ
وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿١٢﴾ يُولِجُ ٱلَّيْلَ فِى ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ
ٱلنَّهَارَ فِى ٱلَّيْلِ وَسَخَّرَ ٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ ۖ كُلٌّ يَجْرِى
لِأَجَلٍ مُّسَمًّى ۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ لَهُ ٱلْمُلْكُ ۚ وَٱلَّذِينَ
تَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ مَا يَمْلِكُونَ مِن قِطْمِيرٍ ﴿١٣﴾ إِن
تَدْعُوهُمْ لَا يَسْمَعُوا۟ دُعَآءَكُمْ وَلَوْ سَمِعُوا۟ مَا ٱسْتَجَابُوا۟ لَكُمْ ۖ
وَيَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يَكْفُرُونَ بِشِرْكِكُمْ ۚ وَلَا يُنَبِّئُكَ مِثْلُ خَبِيرٍ
﴿١٤﴾ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ أَنتُمُ ٱلْفُقَرَآءُ إِلَى ٱللَّهِ ۖ وَٱللَّهُ هُوَ ٱلْغَنِىُّ
ٱلْحَمِيدُ ﴿١٥﴾ إِن يَشَأْ يُذْهِبْكُمْ وَيَأْتِ بِخَلْقٍ جَدِيدٍ ﴿١٦﴾
وَمَا ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ بِعَزِيزٍ ﴿١٧﴾ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٌ وِزْرَ أُخْرَىٰ ۚ وَإِن
تَدْعُ مُثْقَلَةٌ إِلَىٰ حِمْلِهَا لَا يُحْمَلْ مِنْهُ شَىْءٌ وَلَوْ كَانَ ذَا قُرْبَىٰ ۗ
إِنَّمَا تُنذِرُ ٱلَّذِينَ يَخْشَوْنَ رَبَّهُم بِٱلْغَيْبِ وَأَقَامُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ ۚ
وَمَن تَزَكَّىٰ فَإِنَّمَا يَتَزَكَّىٰ لِنَفْسِهِۦ ۚ وَإِلَى ٱللَّهِ ٱلْمَصِيرُ ﴿١٨﴾

(12) Koguna biyu ba za su daidaita ba, wannan na da dadin gaske da saukin hadiya, wannan kuma mai zartsin gaske ne, daga kowannensu kuma kuna cin nama sabo (ba bushasshe ba), kuna kuma fito da kayan ado (daga gare su) wanda kuke sawa; kuma kana ganin jiragen ruwa suna keta shi (kogin) don ku nemi falalarsa don kuma ku gode (masa)

(13) Yana shigar da dare cikin yini, Yana kuma shigar da yini cikin dare, Ya kuma hore rana da wata kowannensu yana tafiya zuwa ga ajali iyakantacce. (Mai yin wannan kuwa) Shi ne Allah Ubangijinku, mulki (kuwa) nasa ne. Wadanda kuwa kuke bauta wa ba Shi ba, ba su mallaki ko da rigar kwallon dabino ba

(14) Idan kuna kiran su, ba sa jin kiranku, ko da ma sun ji, ba za su amsa muku ba; a ranar alkiyama kuma za su butulce wa shirkarku. Ba kuwa mai ba ka labari kamar cikakken Masani

(15) Ya ku mutane, ku ne mabukata a wurin Allah; Allah kuma Shi ne Mawadaci, Sha-yabo

(16) Idan Ya ga dama sai Ya tafiyar da ku Ya kawo wata sabuwar halittar

(17) Wannan kuwa ba wani abu ne ba da zai gagari Allah

(18) Kuma wani mai daukar nauyi ba ya daukan laifin wani. Idan kuma wani mai nannauyan zunubi ya yi kira zuwa dauke nauyin nasa, ba za a dauke masa komai daga nauyin ba, ko da kuwa dan'uwa ne makusanci. Kai dai kana mai gargadi ne kawai ga wadanda suke tsoron Ubangijinsu ba tare da ganin Sa ba, suka kuma tsai da salla. Wanda kuwa ya tsarkaka, to ya tsarkaka ne don kansa. Makoma kuma na ga Allah Shi kadai

وَمَا يَسْتَوِي ٱلْأَعْمَىٰ وَٱلْبَصِيرُ ﴿١٩﴾ وَلَا ٱلظُّلُمَٰتُ وَلَا ٱلنُّورُ
﴿٢٠﴾ وَلَا ٱلظِّلُّ وَلَا ٱلْحَرُورُ ﴿٢١﴾ وَمَا يَسْتَوِي ٱلْأَحْيَآءُ وَلَا
ٱلْأَمْوَٰتُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُسْمِعُ مَن يَشَآءُ ۖ وَمَآ أَنتَ بِمُسْمِعٍ مَّن فِي
ٱلْقُبُورِ ﴿٢٢﴾ إِنْ أَنتَ إِلَّا نَذِيرٌ ﴿٢٣﴾ إِنَّآ أَرْسَلْنَٰكَ بِٱلْحَقِّ بَشِيرًا
وَنَذِيرًا ۚ وَإِن مِّنْ أُمَّةٍ إِلَّا خَلَا فِيهَا نَذِيرٌ ﴿٢٤﴾ وَإِن يُكَذِّبُوكَ
فَقَدْ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ جَآءَتْهُمْ رُسُلُهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ
وَبِٱلزُّبُرِ وَبِٱلْكِتَٰبِ ٱلْمُنِيرِ ﴿٢٥﴾ ثُمَّ أَخَذْتُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ۖ
فَكَيْفَ كَانَ نَكِيرِ ﴿٢٦﴾ أَلَمْ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ
مَآءً فَأَخْرَجْنَا بِهِۦ ثَمَرَٰتٍ مُّخْتَلِفًا أَلْوَٰنُهَا ۚ وَمِنَ ٱلْجِبَالِ
جُدَدٌۢ بِيضٌ وَحُمْرٌ مُّخْتَلِفٌ أَلْوَٰنُهَا وَغَرَابِيبُ سُودٌ ﴿٢٧﴾
وَمِنَ ٱلنَّاسِ وَٱلدَّوَآبِّ وَٱلْأَنْعَٰمِ مُخْتَلِفٌ أَلْوَٰنُهُۥ كَذَٰلِكَ ۗ
إِنَّمَا يَخْشَى ٱللَّهَ مِنْ عِبَادِهِ ٱلْعُلَمَٰٓؤُا۟ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ غَفُورٌ ﴿٢٨﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ يَتْلُونَ كِتَٰبَ ٱللَّهِ وَأَقَامُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَأَنفَقُوا۟ مِمَّا
رَزَقْنَٰهُمْ سِرًّا وَعَلَانِيَةً يَرْجُونَ تِجَٰرَةً لَّن تَبُورَ ﴿٢٩﴾ لِيُوَفِّيَهُمْ
أُجُورَهُمْ وَيَزِيدَهُم مِّن فَضْلِهِۦٓ ۚ إِنَّهُۥ غَفُورٌ شَكُورٌ ﴿٣٠﴾

(19) Makaho da mai gani ba za su yi daidai ba
(20)Da kuma duhu da haske (ba za su yi daidai ba)
(21) Da kuma inuwa da zafin (rana) (ba za su yi daidai ba)
(22) Kuma rayayyu da matattu ba za su yi daidai ba. Lalle Allah Yana jiyar da wanda Ya ga dama; kai kuma ba mai iya jiyar da waɗanda suke cikin ƙaburbura ne ba
(23) Kai ba kowa ba ne face mai gargaɗi
(24) Lalle Mu Muka aiko ka da gaskiya kana mai albishir mai kuma gargaɗi. Babu kuma wata al'umma da (ta gabata) sai da wani mai gargaɗi ya zo mata
(25) Idan kuwa sun ƙaryata ka, to haƙiƙa waɗanda suka gabace su ma sun ƙaryata, lokacin da manzanninsu suka zo musu da hujjoji da takardu da kuma littattafai masu hasken (shiriya)
(26) Sannan Na damƙi waɗanda suka kafirta; to yaya narkona ya kasance?
(27) Ba ka ganin lalle Allah Ya saukar da ruwa daga sama sai Muka fitar da 'ya'yan itace iri daban-daban da shi? Daga duwatsu kuma (Ya samar da) hanyoyi farare da jajaye masu launi daban-daban da kuma wasu baƙaƙe ƙirin
(28) Daga mutane kuma da dabbobi da kuma dabbobin ni'ima su ma launinsu daban-daban ne kamar waɗancan. Malamai ne kawai suke tsoron Allah daga bayinsa. Lalle Allah Mabuwayi ne Mai gafara
(29) Lalle waɗanda suke karanta Littafin Allah suka kuma tsai da salla suka kuma ciyar daga abin da Muka arzuta su a ɓoye da sarari, suna burin kasuwancin da ba zai yi tazgaro ba
(30) Domin Ya cika musu ladansu Ya kuma ƙara musu daga falalarsa. Lalle Shi Mai gafara ne, Mai godiya

وَٱلَّذِيٓ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ هُوَ ٱلۡحَقُّ مُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ
يَدَيۡهِۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِعِبَادِهِۦ لَخَبِيرُۢ بَصِيرٞ ٣١ ثُمَّ أَوۡرَثۡنَا ٱلۡكِتَٰبَ
ٱلَّذِينَ ٱصۡطَفَيۡنَا مِنۡ عِبَادِنَاۖ فَمِنۡهُمۡ ظَالِمٞ لِّنَفۡسِهِۦ وَمِنۡهُم
مُّقۡتَصِدٞ وَمِنۡهُمۡ سَابِقُۢ بِٱلۡخَيۡرَٰتِ بِإِذۡنِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ هُوَ
ٱلۡفَضۡلُ ٱلۡكَبِيرُ ٣٢ جَنَّٰتُ عَدۡنٖ يَدۡخُلُونَهَا يُحَلَّوۡنَ
فِيهَا مِنۡ أَسَاوِرَ مِن ذَهَبٖ وَلُؤۡلُؤٗاۖ وَلِبَاسُهُمۡ فِيهَا حَرِيرٞ ٣٣
وَقَالُواْ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِيٓ أَذۡهَبَ عَنَّا ٱلۡحَزَنَۖ إِنَّ رَبَّنَا لَغَفُورٞ
شَكُورٌ ٣٤ ٱلَّذِيٓ أَحَلَّنَا دَارَ ٱلۡمُقَامَةِ مِن فَضۡلِهِۦ لَا يَمَسُّنَا
فِيهَا نَصَبٞ وَلَا يَمَسُّنَا فِيهَا لُغُوبٞ ٣٥ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَهُمۡ
نَارُ جَهَنَّمَۖ لَا يُقۡضَىٰ عَلَيۡهِمۡ فَيَمُوتُواْ وَلَا يُخَفَّفُ عَنۡهُم مِّنۡ
عَذَابِهَاۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي كُلَّ كَفُورٖ ٣٦ وَهُمۡ يَصۡطَرِخُونَ
فِيهَا رَبَّنَآ أَخۡرِجۡنَا نَعۡمَلۡ صَٰلِحًا غَيۡرَ ٱلَّذِي كُنَّا نَعۡمَلُۚ
أَوَلَمۡ نُعَمِّرۡكُمۡ مَّا يَتَذَكَّرُ فِيهِ مَن تَذَكَّرَ وَجَآءَكُمُ ٱلنَّذِيرُۖ
فَذُوقُواْ فَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِن نَّصِيرٍ ٣٧ إِنَّ ٱللَّهَ عَٰلِمُ
غَيۡبِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٣٨

(31) Kuma abin da Muka yiwo maka wahayinsa na Littafi shi ne gaskiya, yana gaskata abin da yake gabaninsa (na littattafai). Lalle Allah game da bayinsa Masani ne, Mai gani

(32) Sannan Muka gadar da Littafin ga waɗanda Muka zaɓa cikin bayinmu; to daga cikinsu akwai mai cutar kansa(1), akwai kuma mai tsakaitawa a cikinsu(2), kuma akwai wanda ya yi fintinkau a aikata alheri(3) da izinin Allah. Wannan kuwa shi ne falala mai girma

(33) (Watau) gidajen Aljanna na dawwama da za su shige su, za a yi musu ado a cikinsu na awarwaron zinare da kuma lu'ulu'u; tufafinsu a cikinsu (gidajen Aljanna) alharini ne

(34) Kuma Su ce: "Yabo ya tabbata ga Allah Wanda Ya yaye mana baƙin ciki; lalle Ubangijinmu Mai gafara ne, Mai godiya

(35) "Wanda Ya saukar da mu a gidan dawwama don falalarsa, ba wata wahala da za ta shafe mu a cikinsa, kuma ba wata gajiya da za ta shafe mu a cikinsa."

(36) Waɗanda kuwa suka kafirta suna da (sakamakon) wutar Jahannama, ba za a karɓi rayukansu ba balle su mutu, ba kuma za a sauƙaƙa musu wani abu daga azabarta ba. Kamar haka Muke saka wa kowanne kafiri

(37) Su kuwa suna ta kururuwa a cikinta suna cewa: "Ya Ubangijinmu, Ka fitar da mu, za mu yi aiki nagari, ba irin wanda muka kasance muna aikatawa ba." (Sai a ce da su): "Yanzu ba Mu raya ku ba gwargwadon lokacin da mai wa'azantuwa zai wa'azantu, kuma mai gargaɗi ya zo muku? Sai ku ɗanɗani (azaba), sannan azzalumai ba su da wani mataimaki."

(38) Lalle Allah Masanin gaibin sammai da ƙasa ne. Lalle Shi Masanin abubuwan da suke cikin zukata ne

(1) Watau ta hanyar aikata laifuffukan da ba su kai kafirci ba.

(2) Watau masu aikata wajibai da guje wa haramun ba tare da sun kula da mustahabbai ba.

(3) Su ne waxanda suka haxa da aikata mustahabbai da barin makruhi.

هُوَ ٱلَّذِى جَعَلَكُمْ خَلَٰٓئِفَ فِى ٱلْأَرْضِ ۚ فَمَن كَفَرَ فَعَلَيْهِ كُفْرُهُۥ ۖ وَلَا
يَزِيدُ ٱلْكَٰفِرِينَ كُفْرُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ إِلَّا مَقْتًا ۖ وَلَا يَزِيدُ ٱلْكَٰفِرِينَ
كُفْرُهُمْ إِلَّا خَسَارًا ﴿٣٩﴾ قُلْ أَرَءَيْتُمْ شُرَكَآءَكُمُ ٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن
دُونِ ٱللَّهِ أَرُونِى مَاذَا خَلَقُوا۟ مِنَ ٱلْأَرْضِ أَمْ لَهُمْ شِرْكٌ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
أَمْ ءَاتَيْنَٰهُمْ كِتَٰبًا فَهُمْ عَلَىٰ بَيِّنَتٍ مِّنْهُ ۚ بَلْ إِن يَعِدُ ٱلظَّٰلِمُونَ
بَعْضُهُم بَعْضًا إِلَّا غُرُورًا ﴿٤٠﴾ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ يُمْسِكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضَ أَن تَزُولَا ۚ وَلَئِن زَالَتَآ إِنْ أَمْسَكَهُمَا مِنْ أَحَدٍ مِّنۢ بَعْدِهِۦٓ ۚ
إِنَّهُۥ كَانَ حَلِيمًا غَفُورًا ﴿٤١﴾ وَأَقْسَمُوا۟ بِٱللَّهِ جَهْدَ أَيْمَٰنِهِمْ لَئِن جَآءَهُمْ
نَذِيرٌ لَّيَكُونُنَّ أَهْدَىٰ مِنْ إِحْدَى ٱلْأُمَمِ ۖ فَلَمَّا جَآءَهُمْ نَذِيرٌ
مَّا زَادَهُمْ إِلَّا نُفُورًا ﴿٤٢﴾ ٱسْتِكْبَارًا فِى ٱلْأَرْضِ وَمَكْرَ ٱلسَّيِّئِ ۚ
وَلَا يَحِيقُ ٱلْمَكْرُ ٱلسَّيِّئُ إِلَّا بِأَهْلِهِۦ ۚ فَهَلْ يَنظُرُونَ إِلَّا سُنَّتَ
ٱلْأَوَّلِينَ ۚ فَلَن تَجِدَ لِسُنَّتِ ٱللَّهِ تَبْدِيلًا ۖ وَلَن تَجِدَ لِسُنَّتِ ٱللَّهِ تَحْوِيلًا
﴿٤٣﴾ أَوَلَمْ يَسِيرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ فَيَنظُرُوا۟ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن
قَبْلِهِمْ وَكَانُوٓا۟ أَشَدَّ مِنْهُمْ قُوَّةً ۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُعْجِزَهُۥ مِن شَىْءٍ
فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِى ٱلْأَرْضِ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ عَلِيمًا قَدِيرًا ﴿٤٤﴾

(39) Shi ne wanda Ya sanya ku halifofi a bayan ƙasa. Saboda haka wanda ya kafirta sakamakon kafircinsa yana kansa, kuma kafircin kafirai ba zai ƙara musu komai ba a wurin Ubangijinsu sai ƙiyayya; kuma kafircin kafirai ba zai ƙara musu komai ba sai hasara

(40) Ka ce: "Ku ba ni labarin abokan tarayyar naku da kuke bauta wa ba Allah ba, ku nuna min abin da suka halitta daga ƙasa, ko kuma suna da wata tarayya ne a cikin (halittar) sammai, ko kuma Mun ba su wani littafi ne, saboda haka suke da wata hujja daga wajensa?" Ba haka ba ne, ba dai abin da azzalumai suke wa juna alƙawari da shi in ban da rudi

(41) Lalle Allah ne Yake riƙe da sammai da ƙasa don kada su ruguje. Lallai kuwa idan da za su ruguje, to ba wani mai riƙe su in ba Shi ba. Lalle Shi (Allah) Ya kasance Mai haƙuri ne, Mai gafara

(42) Suka kuma rantse da Allah iya rantsuwarsu cewa, lallai idan mai gargaɗi ya zo musu, za su zamanto mafiya shiriya daga ɗayan al'ummu; sannan lokacin da mai gargaɗi ya zo musu ba abin da ya ƙara musu sai nisanta (daga shiriya)

(43) Don girman kai a bayan ƙasa da kuma makirci mummuna. (Sakamakon) makirci mummuna kuwa ba ya sauka sai a kan masu shi. Ba abin da suke saurare in ban da sunnar da ta sami mutanen farko. Sannan ba za ka taɓa samun wani canji ba game da sunnar Allah; kuma ba za ka sami wani sauyi ba game da sunnar Allah

(44) Shin ba su yi tafiya ba ne a cikin ƙasa, sai su ga yaya ƙarshen waɗanda suke gabaninsu ya kasance, alhali kuwa sun zamanto ƙarfafa fiye da su? Ba kuwa wani abu da zai gagari Allah a cikin sammai ko a cikin ƙasa. Lalle Shi Ya kasance Masani ne, Mai iko

وَلَوْ يُؤَاخِذُ ٱللَّهُ ٱلنَّاسَ بِمَا كَسَبُوا۟ مَا تَرَكَ عَلَىٰ ظَهْرِهَا
مِن دَآبَّةٍ وَلَٰكِن يُؤَخِّرُهُمْ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى ۖ فَإِذَا
جَآءَ أَجَلُهُمْ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِعِبَادِهِۦ بَصِيرًۢا ﴿٤٥﴾

سُورَةُ يٰسٓ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يٰسٓ ﴿١﴾ وَٱلْقُرْءَانِ ٱلْحَكِيمِ ﴿٢﴾ إِنَّكَ لَمِنَ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿٣﴾ عَلَىٰ
صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٤﴾ تَنزِيلَ ٱلْعَزِيزِ ٱلرَّحِيمِ ﴿٥﴾ لِتُنذِرَ قَوْمًا
مَّآ أُنذِرَ ءَابَآؤُهُمْ فَهُمْ غَٰفِلُونَ ﴿٦﴾ لَقَدْ حَقَّ ٱلْقَوْلُ عَلَىٰٓ أَكْثَرِهِمْ
فَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿٧﴾ إِنَّا جَعَلْنَا فِىٓ أَعْنَٰقِهِمْ أَغْلَٰلًا فَهِىَ إِلَى
ٱلْأَذْقَانِ فَهُم مُّقْمَحُونَ ﴿٨﴾ وَجَعَلْنَا مِنۢ بَيْنِ أَيْدِيهِمْ سَدًّا
وَمِنْ خَلْفِهِمْ سَدًّا فَأَغْشَيْنَٰهُمْ فَهُمْ لَا يُبْصِرُونَ ﴿٩﴾ وَسَوَآءٌ
عَلَيْهِمْ ءَأَنذَرْتَهُمْ أَمْ لَمْ تُنذِرْهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿١٠﴾ إِنَّمَا تُنذِرُ
مَنِ ٱتَّبَعَ ٱلذِّكْرَ وَخَشِىَ ٱلرَّحْمَٰنَ بِٱلْغَيْبِ ۖ فَبَشِّرْهُ بِمَغْفِرَةٍ
وَأَجْرٍ كَرِيمٍ ﴿١١﴾ إِنَّا نَحْنُ نُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰ وَنَكْتُبُ مَا قَدَّمُوا۟
وَءَاثَٰرَهُمْ ۚ وَكُلَّ شَىْءٍ أَحْصَيْنَٰهُ فِىٓ إِمَامٍ مُّبِينٍ ﴿١٢﴾

(45) Idan da Allah Yana (saurin) damƙar mutane saboda laifin da suka aikata, to da bai bar kowane mai rai ba a bayan ƙasa, sai dai kuma Yana saurara musu ne zuwa wani lokaci ƙayyadajje; to idan lokacin nasu ya zo, to lalle Allah Ya kasance Mai ganin bayinsa ne, (zai kuwa saka musu)

Sura Yasin

(1) YA SIN[1] .
(2) Na rantse da Alƙur'ani mai hikima
(3) Lalle kai (Manzon Allah) tabbas kana daga cikin manzanni
(4) (Kana) a kan tafarki madaidaici
(5) (Alƙur'ani) saukarwar (Allah) Mabuwayi Mai jin ƙai ne
(6) Don ka gargaɗi mutanen da ba a yi wa iyayensu gargaɗi ba[2], don haka kuwa suna cikin gafala
(7) Haƙiƙa hukuncin Allah (na azaba) ya wajaba a kan mafiya yawansu, don ba za su yi imani ba
(8) Lalle Mun sanya ƙuƙumai a wuyoyinsu har zuwa haɓoɓinsu, don haka kawunansu a ɗage suke
(9) Muka kuma sanya wani shamaki a gabansu da kuma shamaki a bayansu, sai Muka lulluɓe musu (idanuwa), don haka ba sa gani
(10)Kuma duk ɗaya ne a wurinsu ko ka yi musu gargaɗi ko ba ka yi musu gargaɗi ba, ba za su yi imani ba
(11) Kana yin gargaɗi ne kawai ga wanda ya bi umarnin Alƙur'ani, ya kuma ji tsoron Allah ba tare da ya gan Shi ba; sai ka yi masa albishir da samun gafara da lada na karamci
(12) Lalle Mu ne za Mu raya matattu, Muke kuma rubuta irin abubuwan da suka gabatar (a rayuwarsu) da kuma abin da suka bari a bayansu (bayan mutuwa). Kowane abu kuma Mun ƙididdige shi a cikin Lauhul-Mahafuzu

(1) Duba Suratul Baqara aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Su ne al'ummar Larabawa waxanda wani annabi bai zo musu ba.

وَٱضۡرِبۡ لَهُم مَّثَلًا أَصۡحَٰبَ ٱلۡقَرۡيَةِ إِذۡ جَآءَهَا ٱلۡمُرۡسَلُونَ
﴿١٣﴾ إِذۡ أَرۡسَلۡنَآ إِلَيۡهِمُ ٱثۡنَيۡنِ فَكَذَّبُوهُمَا فَعَزَّزۡنَا بِثَالِثٖ فَقَالُوٓاْ
إِنَّآ إِلَيۡكُم مُّرۡسَلُونَ ﴿١٤﴾ قَالُواْ مَآ أَنتُمۡ إِلَّا بَشَرٞ مِّثۡلُنَا
وَمَآ أَنزَلَ ٱلرَّحۡمَٰنُ مِن شَيۡءٍ إِنۡ أَنتُمۡ إِلَّا تَكۡذِبُونَ ﴿١٥﴾ قَالُواْ
رَبُّنَا يَعۡلَمُ إِنَّآ إِلَيۡكُمۡ لَمُرۡسَلُونَ ﴿١٦﴾ وَمَا عَلَيۡنَآ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُ
ٱلۡمُبِينُ ﴿١٧﴾ قَالُوٓاْ إِنَّا تَطَيَّرۡنَا بِكُمۡۖ لَئِن لَّمۡ تَنتَهُواْ لَنَرۡجُمَنَّكُمۡ
وَلَيَمَسَّنَّكُم مِّنَّا عَذَابٌ أَلِيمٞ ﴿١٨﴾ قَالُواْ طَٰٓئِرُكُم مَّعَكُمۡۚ أَئِن
ذُكِّرۡتُمۡۚ بَلۡ أَنتُمۡ قَوۡمٞ مُّسۡرِفُونَ ﴿١٩﴾ وَجَآءَ مِنۡ أَقۡصَا ٱلۡمَدِينَةِ
رَجُلٞ يَسۡعَىٰ قَالَ يَٰقَوۡمِ ٱتَّبِعُواْ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ﴿٢٠﴾ ٱتَّبِعُواْ
مَن لَّا يَسۡـَٔلُكُمۡ أَجۡرٗا وَهُم مُّهۡتَدُونَ ﴿٢١﴾ وَمَا لِيَ لَآ أَعۡبُدُ
ٱلَّذِي فَطَرَنِي وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ﴿٢٢﴾ ءَأَتَّخِذُ مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةً
إِن يُرِدۡنِ ٱلرَّحۡمَٰنُ بِضُرّٖ لَّا تُغۡنِ عَنِّي شَفَٰعَتُهُمۡ شَيۡـٔٗا
وَلَا يُنقِذُونِ ﴿٢٣﴾ إِنِّيٓ إِذٗا لَّفِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٍ ﴿٢٤﴾ إِنِّيٓ ءَامَنتُ
بِرَبِّكُمۡ فَٱسۡمَعُونِ ﴿٢٥﴾ قِيلَ ٱدۡخُلِ ٱلۡجَنَّةَۖ قَالَ يَٰلَيۡتَ قَوۡمِي
يَعۡلَمُونَ ﴿٢٦﴾ بِمَا غَفَرَ لِي رَبِّي وَجَعَلَنِي مِنَ ٱلۡمُكۡرَمِينَ ﴿٢٧﴾

(13) Kuma ka ba su misali da mutanen wata alƙarya lokacin da manzannin suka zo mata
(14) A yayin da Muka aika musu (manzanni) biyu sai suka ƙaryata su, sannan Muka ƙarfafe su da na uku, sai suka ce: “Lalle mu manzanni ne zuwa gare ku.”
(15) Suka ce: “Ku ai ba kowa ba ne face mutane kamarmu, kuma (Allah) Mai rahama bai saukar da komai ba, ku dai ba abin da kuke yi sai ƙarya.”
(16) Suka ce: “Ubangijinmu Yana sane da cewa mu lalle tabbas manzanni ne zuwa gare ku
(17) “Kuma babu wani abu a kanmu sai isar da aike bayyananne.”
(18) Suka ce: “Mu dai lalle mun camfa ku, tabbas idan ba ku bari ba to za mu jefe ku, kuma tabbas za ku gamu da azaba mai raɗaɗi daga gare mu.”
(19) Suka ce: “Camfinku ya ƙare a kanku. Yanzu don an yi muku gargaɗi ne (za ku faɗi haka?) A’a, ku dai mutane ne maɓarnata.”
(20) Wani mutum kuma ya zo daga can ƙarshen gari yana sauri ya ce: “Ya ku mutanena, ku bi waɗannan manzannin
(21) “Ku bi waɗanda ba sa tambayar ku wani lada, ga su kuma shiryayyu
(22) “Ni kuma me zai hana ni in bauta wa wanda Ya halicce ni, kuma gare Shi ne za a komar da ku?
(23) “Yanzu na riƙi wasu ababen bauta ba Shi ba, alhali kuwa idan (Allah) Mai rahama Ya nufe ni da wata cuta, cetonsu ba zai amfana min komai ba, kuma ba za su iya tsamo ni ba?
(24) “Lalle ni idan na yi haka to tabbas na zama cikin ɓata mabayyani
(25) “Lalle ni na yi imani da Ubangijinku, sai ku saurare ni.”
(26) Aka ce (da shi): “Shiga Aljanna.” Ya ce: “Kaicon mutanena, ina ma da suna sane?
(27) “Da gafarar da Ubangijina Ya yi min, Ya kuma sanya ni cikin waɗanda aka karrama?”

* وَمَآ أَنزَلْنَا عَلَىٰ قَوْمِهِۦ مِنۢ بَعْدِهِۦ مِن جُندٍ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَمَا
كُنَّا مُنزِلِينَ ﴿٢٨﴾ إِن كَانَتْ إِلَّا صَيْحَةً وَٰحِدَةً فَإِذَا هُمْ خَٰمِدُونَ
﴿٢٩﴾ يَٰحَسْرَةً عَلَى ٱلْعِبَادِ ۚ مَا يَأْتِيهِم مِّن رَّسُولٍ إِلَّا كَانُوا۟ بِهِۦ
يَسْتَهْزِءُونَ ﴿٣٠﴾ أَلَمْ يَرَوْا۟ كَمْ أَهْلَكْنَا قَبْلَهُم مِّنَ ٱلْقُرُونِ
أَنَّهُمْ إِلَيْهِمْ لَا يَرْجِعُونَ ﴿٣١﴾ وَإِن كُلٌّ لَّمَّا جَمِيعٌ لَّدَيْنَا مُحْضَرُونَ
﴿٣٢﴾ وَءَايَةٌ لَّهُمُ ٱلْأَرْضُ ٱلْمَيْتَةُ أَحْيَيْنَٰهَا وَأَخْرَجْنَا مِنْهَا حَبًّا
فَمِنْهُ يَأْكُلُونَ ﴿٣٣﴾ وَجَعَلْنَا فِيهَا جَنَّٰتٍ مِّن نَّخِيلٍ
وَأَعْنَٰبٍ وَفَجَّرْنَا فِيهَا مِنَ ٱلْعُيُونِ ﴿٣٤﴾ لِيَأْكُلُوا۟ مِن ثَمَرِهِۦ
وَمَا عَمِلَتْهُ أَيْدِيهِمْ ۖ أَفَلَا يَشْكُرُونَ ﴿٣٥﴾ سُبْحَٰنَ ٱلَّذِى
خَلَقَ ٱلْأَزْوَٰجَ كُلَّهَا مِمَّا تُنۢبِتُ ٱلْأَرْضُ وَمِنْ أَنفُسِهِمْ
وَمِمَّا لَا يَعْلَمُونَ ﴿٣٦﴾ وَءَايَةٌ لَّهُمُ ٱلَّيْلُ نَسْلَخُ مِنْهُ ٱلنَّهَارَ
فَإِذَا هُم مُّظْلِمُونَ ﴿٣٧﴾ وَٱلشَّمْسُ تَجْرِى لِمُسْتَقَرٍّ لَّهَا ۚ
ذَٰلِكَ تَقْدِيرُ ٱلْعَزِيزِ ٱلْعَلِيمِ ﴿٣٨﴾ وَٱلْقَمَرَ قَدَّرْنَٰهُ مَنَازِلَ حَتَّىٰ
عَادَ كَٱلْعُرْجُونِ ٱلْقَدِيمِ ﴿٣٩﴾ لَا ٱلشَّمْسُ يَنۢبَغِى لَهَآ أَن تُدْرِكَ
ٱلْقَمَرَ وَلَا ٱلَّيْلُ سَابِقُ ٱلنَّهَارِ ۚ وَكُلٌّ فِى فَلَكٍ يَسْبَحُونَ ﴿٤٠﴾

(28) Ba Mu kuma saukar da wata runduna (ta mala'iku) a kan mutanensa daga sama ba a bayansa, ba Mu kuma saba saukarwa ba

(29) Ba abin da ya kasance sai tsawa guda ɗaya, sai ga su matattu

(30) Nadama ta tabbata ga bayi (masu ƙaryatawa), ba wani manzo da zai zo musu sai sun zamanto suna yi masa izgili

(31) Shin ba sa gani ne, al'ummu nawa ne Muka hallaka kafin su, cewa lalle kuwa ba sa dawowa zuwa gare su?

(32) Kuma duk gaba ɗayansu wurinmu za a tattara su

(33) Kuma wata aya ce a gare su (ganin) matacciyar ƙasar da Muka raya ta Muka fitar da ƙwaya daga gare ta, wadda kuma ita ce suke ci

(34) Muka kuma sanya gonaki na dabinai da na inabai a cikinta (ƙasar), Muka kuma ɓuɓɓugo da idanuwan ruwa daga gare ta

(35) Don su ci daga 'ya'yan (itacenta) da kuma abin da hannanyensu suka aikata. Me ya sa ba za su rika godiya ba?

(36) Tsarki ya tabbata ga wanda Ya halicci dangogin komai na maza da mata daga abin da ƙasa take tsirowa, kuma daga su kansu, da ma daga abin da ba su sani ba

(37)Dare ma aya ne a gare su, wanda Muka saɓule yini daga gare shi(1), sai ga su cikin duhu

(38) Rana kuma tana gudu zuwa wurin da aka iyakance mata. Wannan tsari ne na (Allah) Mabuwayi, Masani

(39) Wata kuma Mun ƙaddara masa masaukai, har ya koma kamar tsohuwar zarbar dabino

(40) Ba zai yiwu rana ta riski wata ba, dare kuma ba zai riga yini ba. Kowanne kuwa yana iyo ne a cikin falaki

(1) Watau Allah ( ) yana gusar da rana daga dare sai kawai mutane su gan su cikin duhu.

وَءَايَةٌ لَّهُمْ أَنَّا حَمَلْنَا ذُرِّيَّتَهُمْ فِى ٱلْفُلْكِ ٱلْمَشْحُونِ ﴿٤١﴾ وَخَلَقْنَا
لَهُم مِّن مِّثْلِهِۦ مَا يَرْكَبُونَ ﴿٤٢﴾ وَإِن نَّشَأْ نُغْرِقْهُمْ فَلَا صَرِيخَ لَهُمْ
وَلَا هُمْ يُنقَذُونَ ﴿٤٣﴾ إِلَّا رَحْمَةً مِّنَّا وَمَتَٰعًا إِلَىٰ حِينٍ ﴿٤٤﴾ وَإِذَا
قِيلَ لَهُمُ ٱتَّقُوا۟ مَا بَيْنَ أَيْدِيكُمْ وَمَا خَلْفَكُمْ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ
﴿٤٥﴾ وَمَا تَأْتِيهِم مِّنْ ءَايَةٍ مِّنْ ءَايَٰتِ رَبِّهِمْ إِلَّا كَانُوا۟ عَنْهَا
مُعْرِضِينَ ﴿٤٦﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ أَنفِقُوا۟ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ قَالَ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَنُطْعِمُ مَن لَّوْ يَشَآءُ ٱللَّهُ أَطْعَمَهُۥٓ إِنْ
أَنتُمْ إِلَّا فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٤٧﴾ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلْوَعْدُ إِن كُنتُمْ
صَٰدِقِينَ ﴿٤٨﴾ مَا يَنظُرُونَ إِلَّا صَيْحَةً وَٰحِدَةً تَأْخُذُهُمْ وَهُمْ
يَخِصِّمُونَ ﴿٤٩﴾ فَلَا يَسْتَطِيعُونَ تَوْصِيَةً وَلَآ إِلَىٰٓ أَهْلِهِمْ
يَرْجِعُونَ ﴿٥٠﴾ وَنُفِخَ فِى ٱلصُّورِ فَإِذَا هُم مِّنَ ٱلْأَجْدَاثِ إِلَىٰ رَبِّهِمْ
يَنسِلُونَ ﴿٥١﴾ قَالُوا۟ يَٰوَيْلَنَا مَنۢ بَعَثَنَا مِن مَّرْقَدِنَا ۜ هَٰذَا مَا وَعَدَ
ٱلرَّحْمَٰنُ وَصَدَقَ ٱلْمُرْسَلُونَ ﴿٥٢﴾ إِن كَانَتْ إِلَّا صَيْحَةً
وَٰحِدَةً فَإِذَا هُمْ جَمِيعٌ لَّدَيْنَا مُحْضَرُونَ ﴿٥٣﴾ فَٱلْيَوْمَ لَا تُظْلَمُ
نَفْسٌ شَيْـًٔا وَلَا تُجْزَوْنَ إِلَّا مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٥٤﴾

(41) Kuma wata aya ce a gare su cewa Mu Muka ɗauki iyayensu a cikin jirgin ruwa wanda aka maƙare[1].
(42) Muka kuma halitta musu abin da suke hawa kwatankwacinsa
(43) Idan kuwa da Mun ga dama, sai Mu nutsar da su, don haka babu wani mai taimakon su, ba kuma za a kuɓutar da su ba
(44) Sai dai rahama daga gare Mu da kuma jin dadi zuwa wani lokaci
(45)Idan kuwa aka ce da su: "Ku kiyayi abin da yake gabanku da abin da yake bayanku[2], don a ji ƙan ku",

(sai su bijire)
(46) Babu wata aya daga ayoyin Ubangijinsu da za ta zo musu sai sun kasance masu bijire mata(47) Idan kuma aka ce da su: "Ku ciyar daga abin da Allah Ya arzuta ku," sai waɗanda suka kafirta su ce wa waɗanda suka yi imani: "Yanzu ma ciyar da wanda, da Allah Ya ga dama da ya ciyar da shi? Ba abin da kuke ciki in ban da ɓata mabayyani." (48) Suna kuma cewa: "Yaushe ne wannan alƙawarin, idan kun kasance masu gaskiya?"(49) Ba abin da suke sauraro sai tsawa guda ɗaya da za ta far musu, a yayin da suke cikin hayaniyar rayuwa
(50) Don haka ba za su sami damar yin wata wasiyya ba, kuma ba za su iya koma wa wajen iyalinsu ba(51) Aka kuma busa ƙaho[3], sai ga su suna fitowa daga ƙaburbura zuwa wurin Ubangijinsu (52) Suka ce: "Kaiconmu, wane ne ya tashe mu daga makwancinmu?" (Sai a ce da su): "Ai wannnan shi ne abin da (Allah) Mai rahama Ya yi alƙawarinsa, manzanni kuma sun yi gaskiya."
(53) Ba abin da zai kasance sai tsawa guda ɗaya, sai ga su gaba ɗaya an tattaro su gabanmu
(54) To a yau fa ba za a zalunci wani rai da komai ba, ba kuma za a saka muku ba sai da irin abin da kuka zamanto kuna aikatawa

(1) Watau wanda Allah ya tserar da zuriyar Annabi Adamu ( ) a cikinsa a zamanin Annabi Nuhu ( ) bayan varkewar ruwan Xufana.

(2) Watau ranar lahira da suke fuskanta da abubuwan ban tsoron cikinta, da kuma duniya wadda suke ba ta baya.

(3) Watau busa ta biyu domin tashi.

إِنَّ أَصۡحَٰبَ ٱلۡجَنَّةِ ٱلۡيَوۡمَ فِي شُغُلٖ فَٰكِهُونَ ٥٥ هُمۡ وَأَزۡوَٰجُهُمۡ
فِي ظِلَٰلٍ عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِ مُتَّكِـُٔونَ ٥٦ لَهُمۡ فِيهَا فَٰكِهَةٞ
وَلَهُم مَّا يَدَّعُونَ ٥٧ سَلَٰمٞ قَوۡلٗا مِّن رَّبّٖ رَّحِيمٖ ٥٨ وَٱمۡتَٰزُواْ
ٱلۡيَوۡمَ أَيُّهَا ٱلۡمُجۡرِمُونَ ٥٩ ۞أَلَمۡ أَعۡهَدۡ إِلَيۡكُمۡ يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ
أَن لَّا تَعۡبُدُواْ ٱلشَّيۡطَٰنَۖ إِنَّهُۥ لَكُمۡ عَدُوّٞ مُّبِينٞ ٦٠ وَأَنِ
ٱعۡبُدُونِي هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ ٦١ وَلَقَدۡ أَضَلَّ مِنكُمۡ
جِبِلّٗا كَثِيرًاۖ أَفَلَمۡ تَكُونُواْ تَعۡقِلُونَ ٦٢ هَٰذِهِۦ جَهَنَّمُ ٱلَّتِي
كُنتُمۡ تُوعَدُونَ ٦٣ ٱصۡلَوۡهَا ٱلۡيَوۡمَ بِمَا كُنتُمۡ تَكۡفُرُونَ ٦٤
ٱلۡيَوۡمَ نَخۡتِمُ عَلَىٰٓ أَفۡوَٰهِهِمۡ وَتُكَلِّمُنَآ أَيۡدِيهِمۡ وَتَشۡهَدُ أَرۡجُلُهُم
بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٦٥ وَلَوۡ نَشَآءُ لَطَمَسۡنَا عَلَىٰٓ أَعۡيُنِهِمۡ
فَٱسۡتَبَقُواْ ٱلصِّرَٰطَ فَأَنَّىٰ يُبۡصِرُونَ ٦٦ وَلَوۡ نَشَآءُ لَمَسَخۡنَٰهُمۡ
عَلَىٰ مَكَانَتِهِمۡ فَمَا ٱسۡتَطَٰعُواْ مُضِيّٗا وَلَا يَرۡجِعُونَ
٦٧ وَمَن نُّعَمِّرۡهُ نُنَكِّسۡهُ فِي ٱلۡخَلۡقِۖ أَفَلَا يَعۡقِلُونَ ٦٨
وَمَا عَلَّمۡنَٰهُ ٱلشِّعۡرَ وَمَا يَنۢبَغِي لَهُۥٓۚ إِنۡ هُوَ إِلَّا ذِكۡرٞ وَقُرۡءَانٞ مُّبِينٞ
٦٩ لِّيُنذِرَ مَن كَانَ حَيّٗا وَيَحِقَّ ٱلۡقَوۡلُ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ ٧٠

(55) Lalle ‘yan Aljanna a yau suna cikin shagali, suna masu farin ciki
(56) Su da matansu suna cikin inuwoyi kishingiɗe a kan gadaje
(57) Suna da kayan marmari a cikinta, suna kuma da duk irin abin da suke nema
(58) Sallama (za a rika yi musu), magana ce daga Ubangiji Mai rahama
(59) Kuma (za a ce): “Ku ware a yau, ya ku waɗannan masu manyan laifuka.”
(60) Yanzu ban umarce ku ba, ya ku ‘yan’adam, da cewa kada ku bauta wa Shaiɗan; lalle shi maƙiyi ne mai bayyana (ƙiyayya)?
(61) Kuma ku bauta min. Wannan shi ne tafarki madaidaici
(62) Haƙiƙa kuma (Shaiɗan) ya ɓatar da halittu masu yawa; shin ba za ku hankalta ba?
(63) Wannan ita ce Jahannamar da ta kasance ana yi muku alƙawarinta
(64) Ku shige ta a yau saboda kafircin da kuke yi
(65) A yau za Mu toshe bakunansu, hannayensu su yi mana magana, ƙafafuwansu kuma su ba da shaidar irin abin da suka kasance suna aikatawa
(66) Da kuma Mun ga dama da sai Mu shafe idanuwansu su rika rige-rigen hawan siraɗi, to ta yaya za su iya gani (a wannan lokaci)[1]? (67) Da kuma Mun ga dama da sai Mu jirkita halittarsu a inda suke, saboda haka ba za su iya ci gaba da tafiya ba, ba kuma za su iya dawowa ba[2]
(68) Wanda kuma Muka tsawaita rayuwarsa, za Mu mayar da halittarsa baya[3]; me ya sa ne ba sa hankalta?
(69) Ba Mu kuma koyar da shi (Muhammadu) waƙa ba, kuma ba za ta yiwu ba gare shi. (Abin da ya zo da shi) ba wani abu ba ne sai wa’azi da kuma Alƙur’ani mabayyani
(70) Don ya gargaɗi wanda ya kasance rayayye (wato mumini), azaba kuma ta tabbata a kan kafirai

(1) Watau a shafe idanunsu su daina ganin komai, sannan a umarce su da su yi rige-rigen hawan siraxi zuwa Aljanna, amma ina!

(2) Watau ya jirkita halittarsu ya mayar da su sandararru; ba za su iya yin gaba ba ko baya.

(3) Watau ya koma ya yi rauni na jiki da na qwaqwalwa.

أَوَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّا خَلَقْنَا لَهُم مِّمَّا عَمِلَتْ أَيْدِينَآ أَنْعَٰمًا فَهُمْ لَهَا
مَٰلِكُونَ ﴿٧١﴾ وَذَلَّلْنَٰهَا لَهُمْ فَمِنْهَا رَكُوبُهُمْ وَمِنْهَا يَأْكُلُونَ
﴿٧٢﴾ وَلَهُمْ فِيهَا مَنَٰفِعُ وَمَشَارِبُ ۖ أَفَلَا يَشْكُرُونَ ﴿٧٣﴾ وَٱتَّخَذُوا۟
مِن دُونِ ٱللَّهِ ءَالِهَةً لَّعَلَّهُمْ يُنصَرُونَ ﴿٧٤﴾ لَا يَسْتَطِيعُونَ
نَصْرَهُمْ وَهُمْ لَهُمْ جُندٌ مُّحْضَرُونَ ﴿٧٥﴾ فَلَا يَحْزُنكَ قَوْلُهُمْ
إِنَّا نَعْلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعْلِنُونَ ﴿٧٦﴾ أَوَلَمْ يَرَ ٱلْإِنسَٰنُ أَنَّا
خَلَقْنَٰهُ مِن نُّطْفَةٍ فَإِذَا هُوَ خَصِيمٌ مُّبِينٌ ﴿٧٧﴾ وَضَرَبَ لَنَا
مَثَلًا وَنَسِىَ خَلْقَهُۥ ۖ قَالَ مَن يُحْىِ ٱلْعِظَٰمَ وَهِىَ رَمِيمٌ ﴿٧٨﴾
قُلْ يُحْيِيهَا ٱلَّذِىٓ أَنشَأَهَآ أَوَّلَ مَرَّةٍ ۖ وَهُوَ بِكُلِّ خَلْقٍ عَلِيمٌ
﴿٧٩﴾ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُم مِّنَ ٱلشَّجَرِ ٱلْأَخْضَرِ نَارًا فَإِذَآ أَنتُم
مِّنْهُ تُوقِدُونَ ﴿٨٠﴾ أَوَلَيْسَ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ
بِقَٰدِرٍ عَلَىٰٓ أَن يَخْلُقَ مِثْلَهُم ۚ بَلَىٰ وَهُوَ ٱلْخَلَّٰقُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٨١﴾
إِنَّمَآ أَمْرُهُۥٓ إِذَآ أَرَادَ شَيْـًٔا أَن يَقُولَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿٨٢﴾
فَسُبْحَٰنَ ٱلَّذِى بِيَدِهِۦ مَلَكُوتُ كُلِّ شَىْءٍ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٨٣﴾

سُورَةُ الصَّافَّاتِ



(71) Yanzu ba sa gani ne cewa Mu Muka halitta musu dabbobin ni'ima daga abin da hannanyenmu suka aikata, sai ga su suna mallakar su?
(72) Muka kuma hore musu su, don haka ababen hawansu daga cikinsu ne, kuma daga gare su suke ci
(73) Suna kuma da wata moriya da abin sha daga gare su. Yanzu ba za su rika godiya ba?
(74) Suka kuma riki wasu ababen bauta ba Allah ba, don a taimaka musu
(75) Ba za su iya taimakon su ba, su da gumakan nasu duka ababen tattarawa ne (cikin wuta)
(76) To kada maganarsu ta bakanta maka. Lalle Mu Muna sane da abin da suke boyewa da kuma abin da suke bayyanawa
(77) Yanzu mutum ba ya gani cewa Mu Muka halicce shi daga maniyyi, sai ga shi ya zama mai jayayya a fili?
(78) Ya kuma buga mana misali, kuma ya manta da halittarsa (yayin da) ya ce: "Wane ne zai raya kasusuwa, alhali kuma sun rududduge?
(79) Ka ce: "Wannan da Ya fare su tun farko Shi ne zai raya su; Shi kuwa Masanin kowacce irin halitta ne
(80) "Wanda kuma Ya samar muku wuta daga koriyar bishiya, sai ga shi kuna hura wuta daga gare ta."
(81) Yanzu wanda Ya halacci sammai da kasa ba zai zama Mai ikon halitta irinsu ba? Ai tabbas zai iya, kuma Shi ne Mai yawan yin halitta, Masani
(82) Umarninsa kawai idan Ya yi nufin wani abu sai Ya ce da shi: "Kasance", sai ya kasance
(83) To tsarki ya tabbata ga wanda mulkin kowane abu yake a hannunsa, kuma wurinsa ne kawai za a komar da ku

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلصَّٰٓفَّٰتِ صَفًّا ﴿١﴾ فَٱلزَّٰجِرَٰتِ زَجْرًا ﴿٢﴾ فَٱلتَّٰلِيَٰتِ ذِكْرًا ﴿٣﴾ إِنَّ
إِلَٰهَكُمْ لَوَٰحِدٌ ﴿٤﴾ رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا وَرَبُّ
ٱلْمَشَٰرِقِ ﴿٥﴾ إِنَّا زَيَّنَّا ٱلسَّمَآءَ ٱلدُّنْيَا بِزِينَةٍ ٱلْكَوَاكِبِ ﴿٦﴾ وَحِفْظًا
مِّن كُلِّ شَيْطَٰنٍ مَّارِدٍ ﴿٧﴾ لَّا يَسَّمَّعُونَ إِلَى ٱلْمَلَإِ ٱلْأَعْلَىٰ وَيُقْذَفُونَ
مِن كُلِّ جَانِبٍ ﴿٨﴾ دُحُورًا وَلَهُمْ عَذَابٌ وَاصِبٌ ﴿٩﴾ إِلَّا مَنْ خَطِفَ
ٱلْخَطْفَةَ فَأَتْبَعَهُۥ شِهَابٌ ثَاقِبٌ ﴿١٠﴾ فَٱسْتَفْتِهِمْ أَهُمْ أَشَدُّ خَلْقًا أَم
مَّنْ خَلَقْنَآ ۚ إِنَّا خَلَقْنَٰهُم مِّن طِينٍ لَّازِبٍ ﴿١١﴾ بَلْ عَجِبْتَ وَيَسْخَرُونَ
﴿١٢﴾ وَإِذَا ذُكِّرُوا۟ لَا يَذْكُرُونَ ﴿١٣﴾ وَإِذَا رَأَوْا۟ ءَايَةً يَسْتَسْخِرُونَ ﴿١٤﴾
وَقَالُوٓا۟ إِنْ هَٰذَآ إِلَّا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿١٥﴾ أَءِذَا مِتْنَا وَكُنَّا تُرَابًا وَعِظَٰمًا
أَءِنَّا لَمَبْعُوثُونَ ﴿١٦﴾ أَوَءَابَآؤُنَا ٱلْأَوَّلُونَ ﴿١٧﴾ قُلْ نَعَمْ وَأَنتُمْ دَٰخِرُونَ
﴿١٨﴾ فَإِنَّمَا هِىَ زَجْرَةٌ وَٰحِدَةٌ فَإِذَا هُمْ يَنظُرُونَ ﴿١٩﴾ وَقَالُوا۟ يَٰوَيْلَنَا
هَٰذَا يَوْمُ ٱلدِّينِ ﴿٢٠﴾ هَٰذَا يَوْمُ ٱلْفَصْلِ ٱلَّذِى كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ﴿٢١﴾
۞ ٱحْشُرُوا۟ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ وَأَزْوَٰجَهُمْ وَمَا كَانُوا۟ يَعْبُدُونَ ﴿٢٢﴾ مِن دُونِ
ٱللَّهِ فَٱهْدُوهُمْ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلْجَحِيمِ ﴿٢٣﴾ وَقِفُوهُمْ ۖ إِنَّهُم مَّسْـُٔولُونَ ﴿٢٤﴾

Sura Saffat

(1) Ina rantsuwa da mala'iku masu yin sahu-sahu
(2) Sannan da masu yi wa girgije tsawa
(3) Da masu karanta maganar Allah
(4) Lalle Ubangiijnku tabbas Daya ne
(5) Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, kuma Ubangijin wuraren hudowar rana
(6) Lalle Mun ƙawata sama ta kusa da ado na taurari
(7) Da kuma tsaro daga dukkan wani shaiɗan mai tsaurin kai.
(8) Ba kuma za su iya jiyowa ba (daga asirin) mala'iku na sama, sai a yi ta jifan su ta kowane ɓangare
(9) Don kora; suna kuma da wata azaba dawwamamma
(10) Sai dai wanda ya yi fautowar jin, to sai wani tauraro mai haske da ƙuna ya biyo shi
(11) Ka tambaye su cewa, yanzu su suka fi ƙarfin halitta ko kuwa waɗanda a da Muka halitta? Lalle Mu Mun halicce su daga wani taɓo mai danƙo (12) A'a, kai dai ka yi mamakin (ikon Allah da ƙaryatawarsu) ne, su kuma suna yin izgili
(13) Idan kuma aka yi musu wa'azi ba sa wa'azantuwa
(14) Idan kuma suka ga wata aya sai su tsananta ba'a
(15) Su kuma ce: "Wannan ba wani abu ba ne in ban da sihiri mabayyani
(16) "Yanzu idan muka mutu muka zama ƙasa da ƙasusuwa shin da gaske za a tashe mu?
(17)"Haka ma da iyayenmu na farko?"
(18) Ka ce: "Na'am, (za a tashe ku) kuna kuwa ƙasƙantattu."
(19) To (wannan) ba wani abu ba ne sai kawai tsawa guda ɗaya, sai ga su suna sauraron (abin da zai faru)
(20) Dirán (tras resucitar): "¡Ay de nosotros! Este es el Día del Juicio Final".
(21) "Wannan ita ce ranar hukunci wadda kuka kasance kuna ƙaryatawa."
(22) (Za a ce da mala'iku): "Ku tattaro waɗanda suka yi zalunci su da abokan haɗinsu (shaiɗanu) da kuma abin da suka kasance suna bauta wa
(23) Waɗanda ba Allah ba, sai ku nuna musu hanyar zuwa wutar Jahima

مَا لَكُمْ لَا تَنَاصَرُونَ ﴿٢٥﴾ بَلْ هُمُ ٱلْيَوْمَ مُسْتَسْلِمُونَ ﴿٢٦﴾ وَأَقْبَلَ بَعْضُهُمْ
عَلَىٰ بَعْضٍ يَتَسَآءَلُونَ ﴿٢٧﴾ قَالُوٓاْ إِنَّكُمْ كُنتُمْ تَأْتُونَنَا عَنِ ٱلْيَمِينِ ﴿٢٨﴾
قَالُواْ بَل لَّمْ تَكُونُواْ مُؤْمِنِينَ ﴿٢٩﴾ وَمَا كَانَ لَنَا عَلَيْكُم مِّن سُلْطَٰنٍۖ
بَلْ كُنتُمْ قَوْمًا طَٰغِينَ ﴿٣٠﴾ فَحَقَّ عَلَيْنَا قَوْلُ رَبِّنَآۖ إِنَّا لَذَآئِقُونَ ﴿٣١﴾
فَأَغْوَيْنَٰكُمْ إِنَّا كُنَّا غَٰوِينَ ﴿٣٢﴾ فَإِنَّهُمْ يَوْمَئِذٍ فِى ٱلْعَذَابِ مُشْتَرِكُونَ
﴿٣٣﴾ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَفْعَلُ بِٱلْمُجْرِمِينَ ﴿٣٤﴾ إِنَّهُمْ كَانُوٓاْ إِذَا قِيلَ لَهُمْ
لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ يَسْتَكْبِرُونَ ﴿٣٥﴾ وَيَقُولُونَ أَئِنَّا لَتَارِكُوٓاْ ءَالِهَتِنَا
لِشَاعِرٍ مَّجْنُونٍ ﴿٣٦﴾ بَلْ جَآءَ بِٱلْحَقِّ وَصَدَّقَ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿٣٧﴾ إِنَّكُمْ
لَذَآئِقُواْ ٱلْعَذَابِ ٱلْأَلِيمِ ﴿٣٨﴾ وَمَا تُجْزَوْنَ إِلَّا مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ
﴿٣٩﴾ إِلَّا عِبَادَ ٱللَّهِ ٱلْمُخْلَصِينَ ﴿٤٠﴾ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمْ رِزْقٌ مَّعْلُومٌ ﴿٤١﴾
فَوَٰكِهُ وَهُم مُّكْرَمُونَ ﴿٤٢﴾ فِى جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ﴿٤٣﴾ عَلَىٰ سُرُرٍ مُّتَقَٰبِلِينَ
﴿٤٤﴾ يُطَافُ عَلَيْهِم بِكَأْسٍ مِّن مَّعِينٍ ﴿٤٥﴾ بَيْضَآءَ لَذَّةٍ لِّلشَّٰرِبِينَ
﴿٤٦﴾ لَا فِيهَا غَوْلٌ وَلَا هُمْ عَنْهَا يُنزَفُونَ ﴿٤٧﴾ وَعِندَهُمْ قَٰصِرَٰتُ
ٱلطَّرْفِ عِينٌ ﴿٤٨﴾ كَأَنَّهُنَّ بَيْضٌ مَّكْنُونٌ ﴿٤٩﴾ فَأَقْبَلَ بَعْضُهُمْ عَلَىٰ
بَعْضٍ يَتَسَآءَلُونَ ﴿٥٠﴾ قَالَ قَآئِلٌ مِّنْهُمْ إِنِّى كَانَ لِى قَرِينٌ ﴿٥١﴾



(25) “Cewa: ‘Me ya sa ba kwa taimakon juna ne?’”
(26) Ba haka ba ne, su dai a yau masu mika wuya ne
(27) Shashinsu kuma ya fuskanci shashi suna tambayar juna
(28) Suka ce: “Lalle kun kasance kuna zo mana ta damanmu[1] (don mu amince muku).”
(29) Suka ce: “A’a, ba ku dai kasance muminai ba ne
(30) “Kuma mu ba mu da wani iko a kanku; ku dai kawai kun kasance mutane ne masu ɗagawa
(31) “Saboda haka faɗar Ubangijinmu (ta azaba) ta tabbata a kanmu; (cewa) lalle tabbas za mu ɗanɗana kuɗarmu (32) “Don haka muka ɓatar da ku, domin mu ma lalle mun kasance ɓatattu ne.’’” (33) Saboda haka su a wannan ranar, masu tarayya ne a cikin azaba (34) Lalle Mu kamar haka Muke yi wa masu manyan laifuka(35) Lalle sun kasance idan aka ce da su: “Babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah,” sai su rika yin girman kai(36) Su kuma rika cewa: “Yanzu ma bar allolinmu don wani mawaki mai tabin hankali?” (37) Ba haka ba ne, ya dai zo ne da gaskiya, ya kuma gaskata manzanni(38) Lalle ku tabbas za ku ɗanɗani azaba mai tsanani(39) Ba kuwa za a saka muku ba sai da irin abin da kuka kasance kuna aikatawa (40) Sai dai bayin Allah waɗanda aka tsarkake (41)Waɗannan suna da arziki sananne(42) (Shi ne) kayan marmari; su kuma ababen karramawa ne(43)A cikin gidajen Aljanna na ni’ima(44) A kan gadaje suna fuskantar juna (45) Ana zagaya su da kofuna na giya
(46) Fara fat, ga kuma daɗi ga masu sha (47) eBabu sa ciwon kai a gare ta, kuma ba za a bugar da su da ita ba (48) A wurinsu kuma akwai mataye masu taƙaita kallonsu ga mazajensu, masu ƙwala-ƙwalan ido(49) Kai ka ce su wani ƙwai ne a cikin kwasfa (50) Sannan sashinsu ya fuskanci shashi suna tambayar juna (51) Wani daga cikinsu ya ce: “Lalle a da can ina da wani aboki

(1) Watau ta hanyar yaudara da daxin baki.

يَقُولُ أَءِنَّكَ لَمِنَ ٱلْمُصَدِّقِينَ ﴿٥٢﴾ أَءِذَا مِتْنَا وَكُنَّا تُرَابًا وَعِظَٰمًا أَءِنَّا
لَمَدِينُونَ ﴿٥٣﴾ قَالَ هَلْ أَنتُم مُّطَّلِعُونَ ﴿٥٤﴾ فَٱطَّلَعَ فَرَءَاهُ فِى سَوَآءِ
ٱلْجَحِيمِ ﴿٥٥﴾ قَالَ تَٱللَّهِ إِن كِدتَّ لَتُرْدِينِ ﴿٥٦﴾ وَلَوْلَا نِعْمَةُ رَبِّى
لَكُنتُ مِنَ ٱلْمُحْضَرِينَ ﴿٥٧﴾ أَفَمَا نَحْنُ بِمَيِّتِينَ ﴿٥٨﴾ إِلَّا مَوْتَتَنَا
ٱلْأُولَىٰ وَمَا نَحْنُ بِمُعَذَّبِينَ ﴿٥٩﴾ إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿٦٠﴾
لِمِثْلِ هَٰذَا فَلْيَعْمَلِ ٱلْعَٰمِلُونَ ﴿٦١﴾ أَذَٰلِكَ خَيْرٌ نُّزُلًا أَمْ شَجَرَةُ
ٱلزَّقُّومِ ﴿٦٢﴾ إِنَّا جَعَلْنَٰهَا فِتْنَةً لِّلظَّٰلِمِينَ ﴿٦٣﴾ إِنَّهَا شَجَرَةٌ
تَخْرُجُ فِىٓ أَصْلِ ٱلْجَحِيمِ ﴿٦٤﴾ طَلْعُهَا كَأَنَّهُۥ رُءُوسُ ٱلشَّيَٰطِينِ
﴿٦٥﴾ فَإِنَّهُمْ لَءَاكِلُونَ مِنْهَا فَمَالِـُٔونَ مِنْهَا ٱلْبُطُونَ ﴿٦٦﴾ ثُمَّ إِنَّ لَهُمْ
عَلَيْهَا لَشَوْبًا مِّنْ حَمِيمٍ ﴿٦٧﴾ ثُمَّ إِنَّ مَرْجِعَهُمْ لَإِلَى ٱلْجَحِيمِ ﴿٦٨﴾
إِنَّهُمْ أَلْفَوْا ءَابَآءَهُمْ ضَآلِّينَ ﴿٦٩﴾ فَهُمْ عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِمْ يُهْرَعُونَ ﴿٧٠﴾
وَلَقَدْ ضَلَّ قَبْلَهُمْ أَكْثَرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٧١﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا فِيهِم
مُّنذِرِينَ ﴿٧٢﴾ فَٱنظُرْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُنذَرِينَ ﴿٧٣﴾
إِلَّا عِبَادَ ٱللَّهِ ٱلْمُخْلَصِينَ ﴿٧٤﴾ وَلَقَدْ نَادَىٰنَا نُوحٌ فَلَنِعْمَ
ٱلْمُجِيبُونَ ﴿٧٥﴾ وَنَجَّيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥ مِنَ ٱلْكَرْبِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٧٦﴾

(52) “Da yake cewa: ‘Yanzu kai kana cikin masu ba da gaskiya?
(53) “Yanzu idan muka mutu muka zama ƙasa da ƙasusuwa shin ko za a iya yi mana wani sakamako?””
(54) Ya ce: “Shin ko za ku leƙa ne?”
(55) Sai shi ya leƙa, sai kuwa ya gan shi a tsakiyar wuta
(56) Ya ce: “Wallahi ka kusa ka hallakar da ni
(57) “Ba don rahamar Ubangijina ba, da lalle ni ma na zama cikin ‘yan wuta.”
(58) (Sai ‘yan Aljanna su ce da juna): “Ashe yanzu ba za mu sake mutuwa ba
?
(59) “Sai fa mutuwarmu ta farko, ba kuma za a azabtar da mu ba?”
(60) Lalle wannan shi ne babban rabo
(61) Don samun irin wannan lalle masu (kyakkyawan) aiki su yi aiki
(62) Shin wannan liyafa ita ce ta fi alheri ko kuwa bishiyar Zaƙƙum?
(63) Lalle Mu Mun sanya ta don ta zama fitina ga azzalumai
(64) Lalle ita wata bishiya ce da take fitowa a tsakiyar wutar Jahima
(65) ‘Ya’yanta kai ka ce kawunan shaiɗanu ne
(66) To su lalle za su ci daga gare ta, za su kuma cika cikkuna da ita
(67) Sannan kuma suna da wani gauraye na tafasasshen ruwa a kanta
(68) Sannan kuma lalle makomarsu wutar Jahima ce
(69) Lalle su sun sami iyayensu ɓatattu
(70) Sai suka riƙa gaggawar bin sawunsu
(71) Haƙiƙa kafin su mafi yawan mutanen farko sun ɓata
(72) Kuma haƙiƙa Mun aiko masu gargaɗi a cikinsu
(73) To ka dubi yadda ƙarshen waɗanda aka yi wa gargaɗi ya kasance
(74) Sai dai bayin Allah waɗanda aka tsarkake
(75) Kuma haƙiƙa Nuhu ya roƙe Mu, to madalla da Masu amsawa
(76) Muka kuma tserar da shi tare da iyalinsa daga baƙin ciki mai girma

وَجَعَلْنَا ذُرِّيَّتَهُۥ هُمُ ٱلْبَاقِينَ ﴿٧٧﴾ وَتَرَكْنَا عَلَيْهِ فِى ٱلْءَاخِرِينَ ﴿٧٨﴾ سَلَٰمٌ
عَلَىٰ نُوحٍ فِى ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٧٩﴾ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجْزِى ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٨٠﴾ إِنَّهُۥ
مِنْ عِبَادِنَا ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٨١﴾ ثُمَّ أَغْرَقْنَا ٱلْءَاخَرِينَ ﴿٨٢﴾ ۞ وَإِنَّ مِن
شِيعَتِهِۦ لَإِبْرَٰهِيمَ ﴿٨٣﴾ إِذْ جَآءَ رَبَّهُۥ بِقَلْبٍ سَلِيمٍ ﴿٨٤﴾ إِذْ قَالَ
لِأَبِيهِ وَقَوْمِهِۦ مَاذَا تَعْبُدُونَ ﴿٨٥﴾ أَئِفْكًا ءَالِهَةً دُونَ ٱللَّهِ تُرِيدُونَ
﴿٨٦﴾ فَمَا ظَنُّكُم بِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٨٧﴾ فَنَظَرَ نَظْرَةً فِى ٱلنُّجُومِ ﴿٨٨﴾
فَقَالَ إِنِّى سَقِيمٌ ﴿٨٩﴾ فَتَوَلَّوْا عَنْهُ مُدْبِرِينَ ﴿٩٠﴾ فَرَاغَ إِلَىٰٓ ءَالِهَتِهِمْ
فَقَالَ أَلَا تَأْكُلُونَ ﴿٩١﴾ مَا لَكُمْ لَا تَنطِقُونَ ﴿٩٢﴾ فَرَاغَ عَلَيْهِمْ ضَرْبًۢا
بِٱلْيَمِينِ ﴿٩٣﴾ فَأَقْبَلُوٓا إِلَيْهِ يَزِفُّونَ ﴿٩٤﴾ قَالَ أَتَعْبُدُونَ مَا تَنْحِتُونَ
﴿٩٥﴾ وَٱللَّهُ خَلَقَكُمْ وَمَا تَعْمَلُونَ ﴿٩٦﴾ قَالُوا۟ ٱبْنُوا۟ لَهُۥ بُنْيَٰنًا فَأَلْقُوهُ
فِى ٱلْجَحِيمِ ﴿٩٧﴾ فَأَرَادُوا۟ بِهِۦ كَيْدًا فَجَعَلْنَٰهُمُ ٱلْأَسْفَلِينَ ﴿٩٨﴾
وَقَالَ إِنِّى ذَاهِبٌ إِلَىٰ رَبِّى سَيَهْدِينِ ﴿٩٩﴾ رَبِّ هَبْ لِى مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ
﴿١٠٠﴾ فَبَشَّرْنَٰهُ بِغُلَٰمٍ حَلِيمٍ ﴿١٠١﴾ فَلَمَّا بَلَغَ مَعَهُ ٱلسَّعْىَ قَالَ يَٰبُنَىَّ
إِنِّىٓ أَرَىٰ فِى ٱلْمَنَامِ أَنِّىٓ أَذْبَحُكَ فَٱنظُرْ مَاذَا تَرَىٰ ۚ قَالَ يَٰٓأَبَتِ
ٱفْعَلْ مَا تُؤْمَرُ ۖ سَتَجِدُنِىٓ إِن شَآءَ ٱللَّهُ مِنَ ٱلصَّٰبِرِينَ ﴿١٠٢﴾

(77) Muka kuma sanya zuriyarsa su ne suka wanzu
(78) Muka kuma bar (kyakkyawan yabo) a gare shi ga ‘yan baya
(79) Aminci ya tabbata ga Nuhu a cikin talikai
(80) Lalle Mu kamar haka Muke saka wa masu kyautatawa
(81) Lalle shi yana daga bayinmu muminai
(82) Sannan Muka nutsar da sauran
(83) Lalle kuma Ibrahimu yana daga mabiya addininsa
(84) A yayin da ya zo wa Ubangijinsa da lafiyayyar zuciya
(85) Lokacin da ya ce da babansa da kuma mutanensa: “Me kuke bauta wa ne?
(86) “Yanzu iyayen giji na ƙarya ba Allah ba kuke nufi?(87) “To mene ne tsammaninku game da Ubangijin talikai?”(88) Sai ya yi duba a cikin taurari, duba na tunani (89) Sannan ya ce: “Lalle ni fa ba ni da lafiya.”(90) Sai suka juya daga wurinsa suna masu ba da baya
(91) Sai ya saɗaɗa zuwa ga gumakansu ya ce (da su): “Yanzu ba za ku ci (abincin da ke gabanku) ba? (92) “Me ya sa ba kwa yin magana ne?” (93) Sai ya yi kansu yana duka da hannunsa na dama
(94) Sai (mutanensa) suka fuskanto shi suna gaggawa (95)Ya ce: “Yanzu kwa riƙa bauta wa abin da kuke sassaƙawa? (96)“Alhali kuwa Allah ne Ya halicce ku, da ma abin da kuke aikatawa?” (97) Suka ce: “Ku gina masa wani gini (ku haɗa wuta a ciki), sannan ku jefa shi cikin wutar.”(98) Sai suka yi nufin sa da mugun shiri, sai Muka mayar da su mafiya ƙasƙanci
(99) Ya kuma ce: “Lalle ni zan yi ƙaura zuwa ga Ubangijina, zai ko shiryar da ni(100) “Ya Ubangijina, Ka yi min baiwa da (ɗa) ya zama daga (mutane) nagari.”(101) Sai Muka yi masa albishir da yaro mai haƙuri(1)
(102) To lokacin da ya kai matsayin yin aiki tare da shi, sai ya ce: “Ya kai ɗana, lalle na ga ina yanka ka a cikin mafarki, sai ka yi tunani me ka gani?” Sai ya ce: “Ya babana, ka aikata duk abin da aka umarce ka, za ka same ni insha Allahu daga cikin masu haƙuri.”

(1) Shi ne xansa Annabi Isma’il ( ).

فَلَمَّآ أَسۡلَمَا وَتَلَّهُۥ لِلۡجَبِينِ ﴿١٠٣﴾ وَنَٰدَيۡنَٰهُ أَن يَٰٓإِبۡرَٰهِيمُ ﴿١٠٤﴾
قَدۡ صَدَّقۡتَ ٱلرُّءۡيَآۚ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ﴿١٠٥﴾ إِنَّ
هَٰذَا لَهُوَ ٱلۡبَلَٰٓؤُاْ ٱلۡمُبِينُ ﴿١٠٦﴾ وَفَدَيۡنَٰهُ بِذِبۡحٍ عَظِيمٖ ﴿١٠٧﴾ وَتَرَكۡنَا
عَلَيۡهِ فِي ٱلۡأٓخِرِينَ ﴿١٠٨﴾ سَلَٰمٌ عَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ ﴿١٠٩﴾ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي
ٱلۡمُحۡسِنِينَ ﴿١١٠﴾ إِنَّهُۥ مِنۡ عِبَادِنَا ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿١١١﴾ وَبَشَّرۡنَٰهُ
بِإِسۡحَٰقَ نَبِيّٗا مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿١١٢﴾ وَبَٰرَكۡنَا عَلَيۡهِ وَعَلَىٰٓ إِسۡحَٰقَۚ
وَمِن ذُرِّيَّتِهِمَا مُحۡسِنٞ وَظَالِمٞ لِّنَفۡسِهِۦ مُبِينٞ ﴿١١٣﴾ وَلَقَدۡ مَنَنَّا
عَلَىٰ مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ﴿١١٤﴾ وَنَجَّيۡنَٰهُمَا وَقَوۡمَهُمَا مِنَ ٱلۡكَرۡبِ
ٱلۡعَظِيمِ ﴿١١٥﴾ وَنَصَرۡنَٰهُمۡ فَكَانُواْ هُمُ ٱلۡغَٰلِبِينَ ﴿١١٦﴾ وَءَاتَيۡنَٰهُمَا
ٱلۡكِتَٰبَ ٱلۡمُسۡتَبِينَ ﴿١١٧﴾ وَهَدَيۡنَٰهُمَا ٱلصِّرَٰطَ ٱلۡمُسۡتَقِيمَ
﴿١١٨﴾ وَتَرَكۡنَا عَلَيۡهِمَا فِي ٱلۡأٓخِرِينَ ﴿١١٩﴾ سَلَٰمٌ عَلَىٰ مُوسَىٰ
وَهَٰرُونَ ﴿١٢٠﴾ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ﴿١٢١﴾ إِنَّهُمَا
مِنۡ عِبَادِنَا ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿١٢٢﴾ وَإِنَّ إِلۡيَاسَ لَمِنَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ﴿١٢٣﴾
إِذۡ قَالَ لِقَوۡمِهِۦٓ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿١٢٤﴾ أَتَدۡعُونَ بَعۡلٗا وَتَذَرُونَ أَحۡسَنَ
ٱلۡخَٰلِقِينَ ﴿١٢٥﴾ ٱللَّهَ رَبَّكُمۡ وَرَبَّ ءَابَآئِكُمُ ٱلۡأَوَّلِينَ ﴿١٢٦﴾

(103) To lokacin da suka sallama wa (Allah), ya kuma kwantar da shi ta ɗaya gefe na goshinsa (da nufin ya yanka shi)
(104) Sai Muka kira shi da cewa: “Ya Ibrahimu
(105) “Haƙiƙa ka gaskata mafarkin.” Lalle Mu kamar haka ne Muke saka wa masu kyautatawa
(106) Lalle wannan tabbas shi ne bala’i ƙarara
(107) Muka kuma fanshe shi da abin yankawa mai girma
(108) Muka kuma bar (kyakkyawan yabo) a gare shi ga ‘yan baya
(109) Aminci ya tabbata ga Ibrahimu
(110) Kamar haka ne Muke saka wa masu kyautatawa.
(111) Lalle shi yana daga cikin bayinmu muminai
(112) Muka kuma yi masa albishir da Is’haƙa a matsayin Annabi daga salihai
(113) Muka kuma yi masa albarka, da kuma Is’haƙa. Daga zuriyarsu kuma akwai mai kyautatawa akwai kuma mai zaluntar kansa a fili (wato kafiri)
(114) Haƙiƙa kuma Mun yi ni’ima ga Musa da Haruna
(115) Muka kuma tserar da su da mutanensu daga babban baƙin ciki
(116) Muka kuma taimake su, sai suka kasance su ne masu rinjaye
(117) Muka kuma ba su Littafi mabayyani (Attaura)
(118) Muka kuma shiryar da su hanya madaidaiciya
(119) Muka kuma bar (kyakkyawan yabo) a gare su ga ‘yan baya
(120) Aminci ya tabbata ga Musa da Haruna
(121) Lalle Mu kamar haka Muke saka wa masu kyautatawa
(122) Lalle suna daga cikin bayinmu muminai
(123) Kuma lalle Ilyasu tabbas yana daga cikin manzanni
(124) Lokacin da ya ce da mutanensa: “Yanzu ba za ku kiyaye dokokin (Allah) ba?
(125) “Yanzu kwa riƙa bauta wa (gunkin) Ba’alu ku riƙa barin Mafi iya kyautata halitta?
(126) “(Wato) Allah Ubangijinku kuma Ubangijin iyayenku na farko?”

فَكَذَّبُوهُ فَإِنَّهُمْ لَمُحْضَرُونَ ﴿١٢٧﴾ إِلَّا عِبَادَ اللَّهِ الْمُخْلَصِينَ ﴿١٢٨﴾
وَتَرَكْنَا عَلَيْهِ فِي الْآخِرِينَ ﴿١٢٩﴾ سَلَامٌ عَلَىٰ إِلْ يَاسِينَ ﴿١٣٠﴾ إِنَّا
كَذَٰلِكَ نَجْزِي الْمُحْسِنِينَ ﴿١٣١﴾ إِنَّهُ مِنْ عِبَادِنَا الْمُؤْمِنِينَ
﴿١٣٢﴾ وَإِنَّ لُوطًا لَمِنَ الْمُرْسَلِينَ ﴿١٣٣﴾ إِذْ نَجَّيْنَاهُ وَأَهْلَهُ أَجْمَعِينَ
﴿١٣٤﴾ إِلَّا عَجُوزًا فِي الْغَابِرِينَ ﴿١٣٥﴾ ثُمَّ دَمَّرْنَا الْآخَرِينَ ﴿١٣٦﴾ وَإِنَّكُمْ
لَتَمُرُّونَ عَلَيْهِم مُّصْبِحِينَ ﴿١٣٧﴾ وَبِاللَّيْلِ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿١٣٨﴾ وَإِنَّ
يُونُسَ لَمِنَ الْمُرْسَلِينَ ﴿١٣٩﴾ إِذْ أَبَقَ إِلَى الْفُلْكِ الْمَشْحُونِ ﴿١٤٠﴾
فَسَاهَمَ فَكَانَ مِنَ الْمُدْحَضِينَ ﴿١٤١﴾ فَالْتَقَمَهُ الْحُوتُ وَهُوَ مُلِيمٌ
﴿١٤٢﴾ فَلَوْلَا أَنَّهُ كَانَ مِنَ الْمُسَبِّحِينَ ﴿١٤٣﴾ لَلَبِثَ فِي بَطْنِهِ إِلَىٰ يَوْمِ
يُبْعَثُونَ ﴿١٤٤﴾ فَنَبَذْنَاهُ بِالْعَرَاءِ وَهُوَ سَقِيمٌ ﴿١٤٥﴾ وَأَنْبَتْنَا
عَلَيْهِ شَجَرَةً مِّن يَقْطِينٍ ﴿١٤٦﴾ وَأَرْسَلْنَاهُ إِلَىٰ مِائَةِ أَلْفٍ أَوْ
يَزِيدُونَ ﴿١٤٧﴾ فَآمَنُوا فَمَتَّعْنَاهُمْ إِلَىٰ حِينٍ ﴿١٤٨﴾ فَاسْتَفْتِهِمْ
أَلِرَبِّكَ الْبَنَاتُ وَلَهُمُ الْبَنُونَ ﴿١٤٩﴾ أَمْ خَلَقْنَا الْمَلَائِكَةَ إِنَاثًا
وَهُمْ شَاهِدُونَ ﴿١٥٠﴾ أَلَا إِنَّهُم مِّنْ إِفْكِهِمْ لَيَقُولُونَ ﴿١٥١﴾ وَلَدَ
اللَّهُ وَإِنَّهُمْ لَكَاذِبُونَ ﴿١٥٢﴾ أَصْطَفَى الْبَنَاتِ عَلَى الْبَنِينَ ﴿١٥٣﴾

(127) Sai suka ƙaryata shi, to don haka, lalle za a halarto da su (wuta)
(128) Sai dai bayin Allah waɗanda aka tsarkake
(129) Muka kuma bar (kyakkyawan yabo) a gare shi ga ‘yan baya
(130) Aminci ya tabbata ga Ilyasu
(131) Lalle Mu kamar haka Muke saka wa masu kyautatawa (132) Lalle shi yana daga bayinmu muminai
(133) Lalle kuma Luɗu tabbas yana daga cikin manzanni
(134) (Ka tuna) sanda Muka tserar da shi tare da iyalinsa baki ɗaya(135) Sai dai wata tsohuwa (wato matarsa) da take cikin halakakku (136) Sannan Muka hallakar da sauran(137) Kuma lalle ku[1]tabbas kuna wucewa ta wajan (gidajensu) da asussuba(138) Da kuma cikin dare. Yanzu ba kwa hankalta ba? (139) Kuma lalle Yunusa tabbas yana daga cikin manzanni (140) (Ka tuna) lokacin da ya gudu zuwa ga jirgin ruwan da yake maƙare(141) Sannan ya shiga ƙuri’a, sai ya zama cikin waɗanda aka yi galaba a kansu (142) Sai kifi ya haɗiye shi, alhali yana abin zargi[2](143) Ba don dai shi ya zama daga masu tsarkake Allah (da yawan tasbihi) ba(144) Tabbas da ya zauna a cikin cikinsa har zuwa ranar da za a tashe su[3](145) Sai Muka jefa shi a tudu, a halin yana cikin rashin lafiya(146) Muka kuma tsirar masa wata bishiya ta kabewa[4] (147)Muka kuma aika shi zuwa ga mutum dubu ɗari, ko kuma sama da haka(148) Sai suka yi imani, sai Muka jiyar da su dadi har zuwa wani lokaci(149) Ka tambaye su: Yanzu Ubangijinka ne Yake da ‘ya’ya mata, su kuma suna da ‘ya’ya maza[5]?(150) Ko kuma Mun halicci mala’iku ne ‘ya’ya mata a gaban idonsu suna gani? (151) Ku saurara! Lalle su saboda ƙaryarsu har suna cewa: (152) ƙ“Allah Ya haihu!” Lalle kuwa su tabbas maƙaryata ne (153) Yanzu Ya zaɓi ‘ya’ya mata a kan ‘ya’ya maza?

(1) Watau ku mutanen Makka.

(2) Watau a kan guduwa ya bar mutanensa ba tare da izinin Allah ba.

(3) Watau ranar alqiyama, domin zai zama shi ne qabarinsa.

(4) Domin ya rufe tsiraicinsa da ganyenta, ya kuma ci ‘ya’yanta, ya kuma sha inuwarta.

(5) Mushirikan Larabawa suna cewa mala’iku mata ne kuma ‘ya’yan Allah ne, yayin da sus uke fifita ‘ya’ya maza ga kawunansu.

مَا لَكُمْ كَيْفَ تَحْكُمُونَ ﴿١٥٤﴾ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ﴿١٥٥﴾ أَمْ لَكُمْ سُلْطَانٌ مُّبِينٌ ﴿١٥٦﴾
فَأْتُوا بِكِتَابِكُمْ إِن كُنتُمْ صَادِقِينَ ﴿١٥٧﴾ وَجَعَلُوا بَيْنَهُ وَبَيْنَ الْجِنَّةِ
نَسَبًا وَلَقَدْ عَلِمَتِ الْجِنَّةُ إِنَّهُمْ لَمُحْضَرُونَ ﴿١٥٨﴾ سُبْحَانَ اللَّهِ عَمَّا
يَصِفُونَ ﴿١٥٩﴾ إِلَّا عِبَادَ اللَّهِ الْمُخْلَصِينَ ﴿١٦٠﴾ فَإِنَّكُمْ وَمَا تَعْبُدُونَ ﴿١٦١﴾
مَا أَنتُمْ عَلَيْهِ بِفَاتِنِينَ ﴿١٦٢﴾ إِلَّا مَنْ هُوَ صَالِ الْجَحِيمِ ﴿١٦٣﴾ وَمَا مِنَّا إِلَّا
لَهُ مَقَامٌ مَّعْلُومٌ ﴿١٦٤﴾ وَإِنَّا لَنَحْنُ الصَّافُّونَ ﴿١٦٥﴾ وَإِنَّا لَنَحْنُ الْمُسَبِّحُونَ
﴿١٦٦﴾ وَإِن كَانُوا لَيَقُولُونَ ﴿١٦٧﴾ لَوْ أَنَّ عِندَنَا ذِكْرًا مِّنَ الْأَوَّلِينَ ﴿١٦٨﴾ لَكُنَّا
عِبَادَ اللَّهِ الْمُخْلَصِينَ ﴿١٦٩﴾ فَكَفَرُوا بِهِ ۖ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ﴿١٧٠﴾ وَلَقَدْ
سَبَقَتْ كَلِمَتُنَا لِعِبَادِنَا الْمُرْسَلِينَ ﴿١٧١﴾ إِنَّهُمْ لَهُمُ الْمَنصُورُونَ ﴿١٧٢﴾
وَإِنَّ جُندَنَا لَهُمُ الْغَالِبُونَ ﴿١٧٣﴾ فَتَوَلَّ عَنْهُمْ حَتَّىٰ حِينٍ ﴿١٧٤﴾ وَأَبْصِرْهُمْ
فَسَوْفَ يُبْصِرُونَ ﴿١٧٥﴾ أَفَبِعَذَابِنَا يَسْتَعْجِلُونَ ﴿١٧٦﴾ فَإِذَا نَزَلَ بِسَاحَتِهِمْ
فَسَاءَ صَبَاحُ الْمُنذَرِينَ ﴿١٧٧﴾ وَتَوَلَّ عَنْهُمْ حَتَّىٰ حِينٍ ﴿١٧٨﴾ وَأَبْصِرْ
فَسَوْفَ يُبْصِرُونَ ﴿١٧٩﴾ سُبْحَانَ رَبِّكَ رَبِّ الْعِزَّةِ عَمَّا يَصِفُونَ
﴿١٨٠﴾ وَسَلَامٌ عَلَى الْمُرْسَلِينَ ﴿١٨١﴾ وَالْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ الْعَالَمِينَ ﴿١٨٢﴾

سُورَةُ صٓ

(154) Me ya same ku, ƙaƙa kuke yin irin wannan hukunci?
(155) Me ya sa ne ba kwa wa'azantuwa?
(156) Ko kuwa kuna da wata hujja ne bayyananniya?
(157) To ku kawo rubutaccen littafinku idan kun kasance masu gaskiya
(158)Suka kuma sanya dangantakar nasaba tsakaninsa da mala'iku. Lalle kuwa su mala'iku sun san cewa tabbas su (masu wannan da'awar) za a kawo su (cikin wuta)(159) Tsarki ya tabbata ga Allah daga abin da suke siffanta (Shi da shi) (160) Sai dai bayin Allah waɗanda aka tsarkake
(161) Lalle ku da abin da kuke bauta wa(162) Ba za ku iya ɓatar da kowa da shi ba (163) Sai dai wanda zai shiga wutar Jahima(164) (Jibrilu ya ce da Mala'iku): "Ba ɗai daga cikinmu face yana da wani matsayi sananne[1]
(165) "Lalle kuma mu masu yin sahu ne(166) "Kuma lalle mu masu yin tasbihi ne." (167) Kuma lalle su (kafirai) sun kasance suna cewa[2]: (168) "Da muna da wani littafi irin na mutanen farko (169) "Tabbas da mun kasance bayin Allah waɗanda aka tsarkake."(170) (Yayin da Alƙur'ani ya zo musu) sai suka kafirce da shi; to ba da daɗewa ba za su sani
(171) Haƙiƙa kuma kalmarmu (ta ba da nasara) ta rigaya ga bayinmu manzanni (172) Lalle su tabbas su ne ababen taimako (173) Kuma lalle rundunarmu tabbas su ne masu yin galaba(174) Sai ka rabu da su har zuwa wani lokaci (175) Kuma ka ganar da su (sakamakon kafirci), sannan ba da daɗewa ba za su gani(176) Yanzu azabarmu suke neman gaggautowa?(177) To lokacin da (azabar) ta sauka a sararin gidajensu, ai asubar waɗanda aka yi wa gargaɗi ta munana(178) Kuma ka rabu da su har zuwa wani lokaci(179) Ka kuma ganar (da su sakamakon kafirci), ba da daɗewa ba za su gani (180) Ubangijinka wanda yake Ubangiji ne Mabuwayi Ya tsarkaka daga abin da suke sifanta (Shi da shi)(181) Aminci kuma ya tabbata bisa ga manzanni (182) Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai

(1) Watau na bautar Allah da yi masa xa'a.

(2) Watau suna cika baki kafin a aiko musu da Manzon Allah ( ).

Sura Sad

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

صٓ وَٱلْقُرْءَانِ ذِى ٱلذِّكْرِ ﴿١﴾ بَلِ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ فِى عِزَّةٍ وَشِقَاقٍ ﴿٢﴾
كَمْ أَهْلَكْنَا مِن قَبْلِهِم مِّن قَرْنٍ فَنَادَوا۟ وَّلَاتَ حِينَ مَنَاصٍ ﴿٣﴾ وَعَجِبُوٓا۟
أَن جَآءَهُم مُّنذِرٌ مِّنْهُمْ ۖ وَقَالَ ٱلْكَٰفِرُونَ هَٰذَا سَٰحِرٌ كَذَّابٌ ﴿٤﴾
أَجَعَلَ ٱلْءَالِهَةَ إِلَٰهًا وَٰحِدًا ۖ إِنَّ هَٰذَا لَشَىْءٌ عُجَابٌ ﴿٥﴾ وَٱنطَلَقَ ٱلْمَلَأُ
مِنْهُمْ أَنِ ٱمْشُوا۟ وَٱصْبِرُوا۟ عَلَىٰٓ ءَالِهَتِكُمْ ۖ إِنَّ هَٰذَا لَشَىْءٌ يُرَادُ ﴿٦﴾
مَا سَمِعْنَا بِهَٰذَا فِى ٱلْمِلَّةِ ٱلْءَاخِرَةِ إِنْ هَٰذَآ إِلَّا ٱخْتِلَٰقٌ ﴿٧﴾ أَءُنزِلَ
عَلَيْهِ ٱلذِّكْرُ مِنۢ بَيْنِنَا ۖ بَلْ هُمْ فِى شَكٍّ مِّن ذِكْرِى ۖ بَل لَّمَّا يَذُوقُوا۟ عَذَابِ
﴿٨﴾ أَمْ عِندَهُمْ خَزَآئِنُ رَحْمَةِ رَبِّكَ ٱلْعَزِيزِ ٱلْوَهَّابِ ﴿٩﴾ أَمْ لَهُم مُّلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا ۖ فَلْيَرْتَقُوا۟ فِى ٱلْأَسْبَٰبِ ﴿١٠﴾ جُندٌ
مَّا هُنَالِكَ مَهْزُومٌ مِّنَ ٱلْأَحْزَابِ ﴿١١﴾ كَذَّبَتْ قَبْلَهُمْ قَوْمُ نُوحٍ
وَعَادٌ وَفِرْعَوْنُ ذُو ٱلْأَوْتَادِ ﴿١٢﴾ وَثَمُودُ وَقَوْمُ لُوطٍ وَأَصْحَٰبُ
لْـَٔيْكَةِ ۖ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلْأَحْزَابُ ﴿١٣﴾ إِن كُلٌّ إِلَّا كَذَّبَ ٱلرُّسُلَ
فَحَقَّ عِقَابِ ﴿١٤﴾ وَمَا يَنظُرُ هَٰٓؤُلَآءِ إِلَّا صَيْحَةً وَٰحِدَةً مَّا لَهَا
مِن فَوَاقٍ ﴿١٥﴾ وَقَالُوا۟ رَبَّنَا عَجِّل لَّنَا قِطَّنَا قَبْلَ يَوْمِ ٱلْحِسَابِ ﴿١٦﴾

(1) SAD[1]. “Na rantse da Alƙur’ani ma’abocin ɗaukaka (2) Sai dai waɗanda suka kafirta suna cikin girman kai ne da jayayya (3) Al’ummu nawa Muka hallaka gabaninsu, sai suka yi ta kururuwar neman agaji, alhali kuwa lokacin ba na neman tsira ba ne (4) Suka kuma yi mamaki don mai gargaɗi ya zo musu daga cikinsu; kuma kafirai suka ce: “Wannan mai sihiri ne babban maƙaryaci (5) “Yanzu yaya zai mayar da alloli Allah guda ɗaya? Lalle wannan abu ne mai ban mamaki.”. (6) Manyansu kuma suka tafi (suna cewa): “Ku yi tafiyarku, kuma ku yi haƙuri a kan (bautar) allolinku; lalle wannan wani shiryayyen abu ne ake nufi (7) “Ba mu taɓa jin irin wannan ba a addinin da ya wuce[2], wannan ba komai ba ne sai ƙage (8) “Yanzu a saukar masa da Alƙur’ani a tsakaninmu?” Ba haka ba ne, su dai suna kokwanto ne game da tunatarwata; bar su, ai har yanzu ba su ɗanɗani azabata ba ne


(9) Ko kuwa a wurinsu ne taskokin rahamar Ubangijinka Mabuwayi Mai baiwa suke? (10) Ko kuma mulkin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu nasu ne? To sai su kama hanyoyin zuwa sama (domin su aikata abin da suke so)

(11) (Waɗannan) wata runduna ce da za a murƙushe ta, kamar sauran al’ummun da suka gabata (waɗanda suka ƙaryata manzanninsu) (12) Mutanen Nuhu sun ƙaryata kafin su (mutan Makka) da Adawa da Fir’auna mai turaku (13) Da kuma Samudawa da mutanen Ludu da mutanen Sarƙaƙiya[3]. Waɗannan su ne al’ummun(14) Babu ɗaya daga cikinsu wanda bai ƙaryata manzanni ba, sai uƙubata ta wajaba (a kansu) (15) Kuma ba abin da waɗannan suke sauraro sai busa guda ɗaya wadda ba ta da makawa (16) Suka kuma ce: “Ya Ubangijinmu, Ka gaggauto mana rabonmu (na azaba) tun kafin ranar hisabi!”

(1) Duba Suratul Baqara aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Watau addinin Annabi Isa ( ).

(3) Su ne mutanen Annabi Shu’aibu ( ).


اصْبِرْ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَاذْكُرْ عَبْدَنَا دَاوُودَ ذَا الْأَيْدِ ۖ إِنَّهُ أَوَّابٌ ﴿١٧﴾ إِنَّا
سَخَّرْنَا الْجِبَالَ مَعَهُ يُسَبِّحْنَ بِالْعَشِيِّ وَالْإِشْرَاقِ ﴿١٨﴾ وَالطَّيْرَ
مَحْشُورَةً ۖ كُلٌّ لَّهُ أَوَّابٌ ﴿١٩﴾ وَشَدَدْنَا مُلْكَهُ وَآتَيْنَاهُ الْحِكْمَةَ
وَفَصْلَ الْخِطَابِ ﴿٢٠﴾ * وَهَلْ أَتَاكَ نَبَأُ الْخَصْمِ إِذْ تَسَوَّرُوا
الْمِحْرَابَ ﴿٢١﴾ إِذْ دَخَلُوا عَلَىٰ دَاوُودَ فَفَزِعَ مِنْهُمْ ۖ قَالُوا لَا تَخَفْ ۖ
خَصْمَانِ بَغَىٰ بَعْضُنَا عَلَىٰ بَعْضٍ فَاحْكُمْ بَيْنَنَا بِالْحَقِّ وَلَا تُشْطِطْ
وَاهْدِنَا إِلَىٰ سَوَاءِ الصِّرَاطِ ﴿٢٢﴾ إِنَّ هَٰذَا أَخِي لَهُ تِسْعٌ وَتِسْعُونَ نَعْجَةً
وَلِيَ نَعْجَةٌ وَاحِدَةٌ فَقَالَ أَكْفِلْنِيهَا وَعَزَّنِي فِي الْخِطَابِ ﴿٢٣﴾ قَالَ
لَقَدْ ظَلَمَكَ بِسُؤَالِ نَعْجَتِكَ إِلَىٰ نِعَاجِهِ ۖ وَإِنَّ كَثِيرًا مِّنَ الْخُلَطَاءِ لَيَبْغِي
بَعْضُهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ إِلَّا الَّذِينَ آمَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ وَقَلِيلٌ
مَّا هُمْ ۗ وَظَنَّ دَاوُودُ أَنَّمَا فَتَنَّاهُ فَاسْتَغْفَرَ رَبَّهُ وَخَرَّ رَاكِعًا وَأَنَابَ ۩
﴿٢٤﴾ فَغَفَرْنَا لَهُ ذَٰلِكَ ۖ وَإِنَّ لَهُ عِندَنَا لَزُلْفَىٰ وَحُسْنَ مَآبٍ ﴿٢٥﴾
يَا دَاوُودُ إِنَّا جَعَلْنَاكَ خَلِيفَةً فِي الْأَرْضِ فَاحْكُم بَيْنَ النَّاسِ بِالْحَقِّ
وَلَا تَتَّبِعِ الْهَوَىٰ فَيُضِلَّكَ عَن سَبِيلِ اللَّهِ ۚ إِنَّ الَّذِينَ يَضِلُّونَ
عَن سَبِيلِ اللَّهِ لَهُمْ عَذَابٌ شَدِيدٌ بِمَا نَسُوا يَوْمَ الْحِسَابِ ﴿٢٦﴾

(17) (Sai Allah Ya ce): “Ka yi haƙuri a kan abin da suke faɗa, ka kuma tuna bawanmu Dawuda ma’abocin ƙarfi; lalle shi ya kasance mai yawan komawa ne (ga Allah)

(18) Lalle Mu Mun hore masa duwatsu suna yin tasbihi tare da shi a yamma da hantsi

(19) Da kuma tsuntsaye a tattare; dukkaninsu suna biyayya a gare shi

(20) Kuma Muka ƙarfafa mulkinsa, Muka kuma ba shi hikima da bayyana hukunce-hukunce (tsakanin masu husuma)

(21) Shin labarin abokan husuma ya zo maka, yayin da suka haura wurin ibada?

(22) Yayin da suka shiga wurin Dawuda sai ya tsorata da su, suka ce: “Kada ka tsorata, (mu biyun nan) masu husuma ne, ɗayanmu ya zalunci ɗaya, sai ka yi hukunci a tsakaninmu da gaskiya, kada kuma ka yi zalunci, kuma ka shiryar da mu hanya madaidaiciya

(23) “Lalle wannan ɗan’uwana ne yana da awaki guda casa’in da tara, ni kuma ina da akuya guda ɗaya, sai ya ce: ‘Ka ba ni ita;’ ya kuma rinjaye ni game da maganar.”

(24) (Dawuda) Ya ce: “Haƙiƙa ya zalunce ka saboda neman haɗe akuyarka cikin awakinsa; kuma lalle yawancin masu haɗa dukiyarsu tabbas wasunsu suna zaluntar wasu, sai fa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, su kuwa kaɗan ne ƙwarai. Sai kuma Dawuda ya tabbata cewa Mun jarraba shi ne, sai ya nemi gafarar Ubangijinsa, ya kuma faɗi yana sujjada kuma ya koma (ga Allah)

(25) Sai Muka gafarta masa wannan; lalle kuma yana da kusanci da Mu da kuma kyakkyawar makoma

(26) Ya Dawuda, lalle Mun sanya ka halifa a bayan ƙasa, sai ka yi hukunci a tsakanin mutane da gaskiya, kada ka bi son zuciya sai ya ɓatar da kai daga hanyar Allah. Lalle waɗanda suke ɓacewa daga hanyar Allah suna da (sakamakon) azaba mai tsanani saboda mantawar da suka yi da ranar hisabi

وَمَا خَلَقْنَا ٱلسَّمَآءَ وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا بَٰطِلًا ۚ ذَٰلِكَ ظَنُّ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ ۚ فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنَ ٱلنَّارِ ﴿٢٧﴾ أَمْ نَجْعَلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟
ٱلصَّٰلِحَٰتِ كَٱلْمُفْسِدِينَ فِى ٱلْأَرْضِ أَمْ نَجْعَلُ ٱلْمُتَّقِينَ كَٱلْفُجَّارِ
﴿٢٨﴾ كِتَٰبٌ أَنزَلْنَٰهُ إِلَيْكَ مُبَٰرَكٌ لِّيَدَّبَّرُوٓا۟ ءَايَٰتِهِۦ وَلِيَتَذَكَّرَ أُو۟لُوا۟
ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿٢٩﴾ وَوَهَبْنَا لِدَاوُۥدَ سُلَيْمَٰنَ ۚ نِعْمَ ٱلْعَبْدُ ۖ إِنَّهُۥٓ أَوَّابٌ
﴿٣٠﴾ إِذْ عُرِضَ عَلَيْهِ بِٱلْعَشِىِّ ٱلصَّٰفِنَٰتُ ٱلْجِيَادُ ﴿٣١﴾ فَقَالَ إِنِّىٓ أَحْبَبْتُ
حُبَّ ٱلْخَيْرِ عَن ذِكْرِ رَبِّى ۖ حَتَّىٰ تَوَارَتْ بِٱلْحِجَابِ ﴿٣٢﴾ رُدُّوهَا عَلَىَّ ۖ
فَطَفِقَ مَسْحًۢا بِٱلسُّوقِ وَٱلْأَعْنَاقِ ﴿٣٣﴾ وَلَقَدْ فَتَنَّا سُلَيْمَٰنَ
وَأَلْقَيْنَا عَلَىٰ كُرْسِيِّهِۦ جَسَدًا ثُمَّ أَنَابَ ﴿٣٤﴾ قَالَ رَبِّ ٱغْفِرْ لِى وَهَبْ
لِى مُلْكًا لَّا يَنۢبَغِى لِأَحَدٍ مِّنۢ بَعْدِىٓ ۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْوَهَّابُ ﴿٣٥﴾
فَسَخَّرْنَا لَهُ ٱلرِّيحَ تَجْرِى بِأَمْرِهِۦ رُخَآءً حَيْثُ أَصَابَ ﴿٣٦﴾ وَٱلشَّيَٰطِينَ
كُلَّ بَنَّآءٍ وَغَوَّاصٍ ﴿٣٧﴾ وَءَاخَرِينَ مُقَرَّنِينَ فِى ٱلْأَصْفَادِ ﴿٣٨﴾ هَٰذَا
عَطَآؤُنَا فَٱمْنُنْ أَوْ أَمْسِكْ بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴿٣٩﴾ وَإِنَّ لَهُۥ عِندَنَا لَزُلْفَىٰ وَحُسْنَ
مَـَٔابٍ ﴿٤٠﴾ وَٱذْكُرْ عَبْدَنَآ أَيُّوبَ إِذْ نَادَىٰ رَبَّهُۥٓ أَنِّى مَسَّنِىَ ٱلشَّيْطَٰنُ
بِنُصْبٍ وَعَذَابٍ ﴿٤١﴾ ٱرْكُضْ بِرِجْلِكَ ۖ هَٰذَا مُغْتَسَلٌۢ بَارِدٌ وَشَرَابٌ ﴿٤٢﴾

(27) Kuma ba Mu halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu a banza ba. Wannan zato ne na waɗanda suka kafirta. Saboda haka tsananin azabar wuta ya tabbata ga waɗanda suka kafirce

(28) Shin za Mu mayar da waɗanda suka yi imani suka yi ayyuka nagari kamar masu ɓarna a bayan ƙasa, ko kuma za Mu mayar da masu taƙawa kamar lalatattu?

(29) Littafi ne mai albarka da Muka saukar maka da shi domin su yi tuntuntuni game da ayoyinsa, don kuma masu hankula su wa'azantu

(30) Muka kuma yi wa Dawuda baiwar (ɗa) Sulaimanu. Madalla da wannan bawan; lalle shi mai yawan komawa ne (ga Sai ya ce: "Lalle ni na fifita son dukiya (watau dawakai) a kan ambaton Ubangijina (watau sallar La'asar) har sai da (rana) ta faɗi."

(33) (Ya ce): "Ku dawo min da su;" sai ya riƙa saran su ta ƙafafu da wuyoyi

(34) Kuma haƙiƙa Mun jarrabi Sulaimanu Muka ɗora wani jiki a kan gadonsa na mulki[1], sannan ya koma (kan mulkinsa)

(35) Ya ce: "Ya Ubangijina, Ka gafarta min, Ka kuma ba ni wani mulki wanda bai kamaci wani ba a bayana ya sami irinsa; lalle Kai Kai ne Mai yawan kyauta."

(36) Sai Muka hore masa iska tana tafiya da umarninsa a natse duk inda ya fuskanta

(37) Da kuma shaiɗanu masu yin kowane irin gini da kuma masu yin nutso (a ruwa)

(38) Wasu kuma an ɗaɗɗaure su cikin maruruwa

(39) Wannan kyautarmu ce, to ka yi kyauta ko ka hana ba da wani bincike ba

(40) Lalle kuma shi tabbas yana da kusanci a wurinmu, da kuma kyakkyawar makoma.

(41) Ka kuma tuna bawanmu Ayyuba lokacin da ya kira Ubangijinsa (yana cewa): "Lalle ni Shaiɗan ya shafe ni da wata wahala da azaba."

(42) (Aka ce da shi): "Ka hauri ƙasa da ƙafarka; (sai ruwa ya ɓuɓɓugo, aka ce da shi): "Wannan ruwan wanka ne mai sanyi da na sha."

(1) (Aka ce da shi): "Ka hauri qasa da qafarka; (sai ruwa ya vuvvugo, aka ce da shi): "Wannan ruwan wanka ne mai sanyi da na sha."

وَوَهَبْنَا لَهُۥٓ أَهْلَهُۥ وَمِثْلَهُم مَّعَهُمْ رَحْمَةً مِّنَّا وَذِكْرَىٰ لِأُو۟لِى ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿٤٣﴾ وَخُذْ بِيَدِكَ ضِغْثًا فَٱضْرِب بِّهِۦ وَلَا تَحْنَثْ ۗ إِنَّا وَجَدْنَٰهُ صَابِرًا ۚ نِّعْمَ ٱلْعَبْدُ ۖ إِنَّهُۥٓ أَوَّابٌ ﴿٤٤﴾ وَٱذْكُرْ عِبَٰدَنَآ إِبْرَٰهِيمَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ أُو۟لِى ٱلْأَيْدِى وَٱلْأَبْصَٰرِ ﴿٤٥﴾ إِنَّآ أَخْلَصْنَٰهُم بِخَالِصَةٍ ذِكْرَى ٱلدَّارِ ﴿٤٦﴾ وَإِنَّهُمْ عِندَنَا لَمِنَ ٱلْمُصْطَفَيْنَ ٱلْأَخْيَارِ ﴿٤٧﴾ وَٱذْكُرْ إِسْمَٰعِيلَ وَٱلْيَسَعَ وَذَا ٱلْكِفْلِ ۖ وَكُلٌّ مِّنَ ٱلْأَخْيَارِ ﴿٤٨﴾ هَٰذَا ذِكْرٌ ۚ وَإِنَّ لِلْمُتَّقِينَ لَحُسْنَ مَـَٔابٍ ﴿٤٩﴾ جَنَّٰتِ عَدْنٍ مُّفَتَّحَةً لَّهُمُ ٱلْأَبْوَٰبُ ﴿٥٠﴾ مُتَّكِـِٔينَ فِيهَا يَدْعُونَ فِيهَا بِفَٰكِهَةٍ كَثِيرَةٍ وَشَرَابٍ ﴿٥١﴾ ۞ وَعِندَهُمْ قَٰصِرَٰتُ ٱلطَّرْفِ أَتْرَابٌ ﴿٥٢﴾ هَٰذَا مَا تُوعَدُونَ لِيَوْمِ ٱلْحِسَابِ ﴿٥٣﴾ إِنَّ هَٰذَا لَرِزْقُنَا مَا لَهُۥ مِن نَّفَادٍ ﴿٥٤﴾ هَٰذَا ۚ وَإِنَّ لِلطَّٰغِينَ لَشَرَّ مَـَٔابٍ ﴿٥٥﴾ جَهَنَّمَ يَصْلَوْنَهَا ۖ فَبِئْسَ ٱلْمِهَادُ ﴿٥٦﴾ هَٰذَا ۖ فَلْيَذُوقُوهُ حَمِيمٌ وَغَسَّاقٌ ﴿٥٧﴾ وَءَاخَرُ مِن شَكْلِهِۦٓ أَزْوَٰجٌ ﴿٥٨﴾ هَٰذَا فَوْجٌ مُّقْتَحِمٌ مَّعَكُمْ ۖ لَا مَرْحَبًۢا بِهِمْ ۚ إِنَّهُمْ صَالُوا۟ ٱلنَّارِ ﴿٥٩﴾ قَالُوا۟ بَلْ أَنتُمْ ۖ لَا مَرْحَبًۢا بِكُمْ ۖ أَنتُمْ قَدَّمْتُمُوهُ لَنَا ۖ فَبِئْسَ ٱلْقَرَارُ ﴿٦٠﴾ قَالُوا۟ رَبَّنَا مَن قَدَّمَ لَنَا هَٰذَا فَزِدْهُ عَذَابًا ضِعْفًا فِى ٱلنَّارِ ﴿٦١﴾

(43) Muka kuma yi masa baiwar iyalinsa da kuma (karin) wasu kamarsu (na `ya`ya da jikoki) don jin ƙai daga gare Mu da kuma wa'azi ga masu hankula

(44) Ka ɗauki danƙi na ciyawa da hannunka ka bugi (matarka da shi)[1], kada ka karya rantsuwarka. Lalle Mun same shi mai haƙuri. Madalla da wannan bawan; lalle shi mai yawan komawa ne (ga Allah)

(45) Ka kuma tuna bayinmu Ibrahimu da Is'haƙa da Yaƙubu ma'abota ƙarfi da basira(46) Lalle Mun keɓance su da wata keɓantacciyar ɗabi'a, (ita ce) tuna lahira(47) Kuma lalle su a wurinmu tabbas suna daga cikin zaɓaɓɓu nagari (48) Ka kuma tuna Isma'ila da Alyasa'u da Zulkifli; dukkaninsu kuma suna cikin zaɓaɓɓu (49) Wannan kyakkyawan ambato ne (a gare su). Kuma lalle masu taƙawa tabbas suna da kyakkyawar makoma (50) (Wato) gidajen Aljannar dawwama, alhali ƙofofi suna buɗe saboda su(51) Suna kishingiɗe a cikinsu, suna kiran a kawo musu ababen marmari masu yawa da abin sha a cikinsu.(52) Kuma a wurinsu akwai tsaraikun mata masu taƙaita kallo (ga mazansu kawai) (53) Wannan shi ne ake yi muku alƙawari da shi a ranar hisabi.(54) Lalle wannan tabbas arzikinmu ne ba mai ƙarewa ba(55) Wannan (shi ne sakamakon masu taƙawa). Kuma lalle masu ɗagawa tabbas suna da mummunar makoma(56) (Wato) Jahannama wadda za su shige ta, to wannan shimfiɗar zama ta munana (57) Wannan (sakamako ne), sai su ɗanɗane shi na tafasasshen ruwa da mugunya (58) Da kuma wani mai kama da shi iri daban-daban(59) (Za a ce da su): "Wannan ma wani gungun ne (na mabiya) mai afkawa tare da ku;" (sai shugabannin su ce): "Ba ma yin maraba da su." Lalle (su duka) wuta za su shiga (60) (Mabiyan kuma sai) su ce: "A'a, ku dai ne ba ma maraba da ku; ku ne kuka kawo mana shi (wannan mummunan sakamako);" to wannan matabbata ta munana(61) Sai suka ce: "Ya Ubangijinmu, duk wanda ya kawo mana wannan (sakamakon) to Ka ƙara masa ninkin azaba a cikin wuta."

(1) Yayin da matarsa ta yi masa laifi ya yi rantsuwa cewa, idan ya warke sai ya yi mata bulala xari. Allah ( ) ya umarce shi da ya cika rantsuwarsa ta wannan hanyar.

وَقَالُوا۟ مَا لَنَا لَا نَرَىٰ رِجَالًا كُنَّا نَعُدُّهُم مِّنَ ٱلْأَشْرَارِ ﴿٦٢﴾ أَتَّخَذْنَٰهُمْ
سِخْرِيًّا أَمْ زَاغَتْ عَنْهُمُ ٱلْأَبْصَٰرُ ﴿٦٣﴾ إِنَّ ذَٰلِكَ لَحَقٌّ تَخَاصُمُ أَهْلِ
ٱلنَّارِ ﴿٦٤﴾ قُلْ إِنَّمَآ أَنَا۠ مُنذِرٌ ۖ وَمَا مِنْ إِلَٰهٍ إِلَّا ٱللَّهُ ٱلْوَٰحِدُ ٱلْقَهَّارُ ﴿٦٥﴾
رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا ٱلْعَزِيزُ ٱلْغَفَّارُ ﴿٦٦﴾ قُلْ هُوَ نَبَؤٌا۟
عَظِيمٌ ﴿٦٧﴾ أَنتُمْ عَنْهُ مُعْرِضُونَ ﴿٦٨﴾ مَا كَانَ لِىَ مِنْ عِلْمٍۭ بِٱلْمَلَإِ ٱلْأَعْلَىٰٓ
إِذْ يَخْتَصِمُونَ ﴿٦٩﴾ إِن يُوحَىٰٓ إِلَىَّ إِلَّآ أَنَّمَآ أَنَا۠ نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿٧٠﴾ إِذْ قَالَ
رَبُّكَ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ إِنِّى خَٰلِقٌۢ بَشَرًا مِّن طِينٍ ﴿٧١﴾ فَإِذَا سَوَّيْتُهُۥ وَنَفَخْتُ
فِيهِ مِن رُّوحِى فَقَعُوا۟ لَهُۥ سَٰجِدِينَ ﴿٧٢﴾ فَسَجَدَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ كُلُّهُمْ
أَجْمَعُونَ ﴿٧٣﴾ إِلَّآ إِبْلِيسَ ٱسْتَكْبَرَ وَكَانَ مِنَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٧٤﴾ قَالَ
يَٰٓإِبْلِيسُ مَا مَنَعَكَ أَن تَسْجُدَ لِمَا خَلَقْتُ بِيَدَىَّ ۖ أَسْتَكْبَرْتَ أَمْ كُنتَ
مِنَ ٱلْعَالِينَ ﴿٧٥﴾ قَالَ أَنَا۠ خَيْرٌ مِّنْهُ خَلَقْتَنِى مِن نَّارٍ وَخَلَقْتَهُۥ مِن طِينٍ
﴿٧٦﴾ قَالَ فَٱخْرُجْ مِنْهَا فَإِنَّكَ رَجِيمٌ ﴿٧٧﴾ وَإِنَّ عَلَيْكَ لَعْنَتِىٓ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلدِّينِ
﴿٧٨﴾ قَالَ رَبِّ فَأَنظِرْنِىٓ إِلَىٰ يَوْمِ يُبْعَثُونَ ﴿٧٩﴾ قَالَ فَإِنَّكَ مِنَ
ٱلْمُنظَرِينَ ﴿٨٠﴾ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْوَقْتِ ٱلْمَعْلُومِ ﴿٨١﴾ قَالَ فَبِعِزَّتِكَ
لَأُغْوِيَنَّهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٨٢﴾ إِلَّا عِبَادَكَ مِنْهُمُ ٱلْمُخْلَصِينَ ﴿٨٣﴾

(62) Suka kuma ce: “Me ya sa ne ba ma ganin wasu mazaje(1) da muka kasance muna lissafa su cikin ashararai?
(63) “Shin mun ɗauke su ne ababen yi wa ba’a (a duniya), ko kuwa idanuwanmu ne suka bauɗe ba sa hango su?”(64) “Shin mun ɗauke su ne ababen yi wa ba’a (a duniya), ko kuwa idanuwanmu ne suka bauɗe ba sa hango su?” (65) Ka ce: “Ni dai mai gargaɗi ne kawai; kuma babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Allah Ɗaya, Mai rinjaye(66) “Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, Mabuwayi, Mai gafara.” (67) Ka ce: “Shi (wannan Alƙur’ani) labari ne mai girma (68) “Da kuke bijire masa (69) “Ban zama na san wani abu ba dangane da mala’iku masu daraja lokacin da suke yin muhawara (game da halittar Adamu)
(70) “Ba wani wahayi da aka yiwo min sai kawai cewa ni mai gargaɗi ne mai bayyanawa.”(71) (Ka tuna) lokacin da Ubangijinka Ya ce da mala’iku: “Lalle Ni zan halicci wani mutum daga taɓo
(72) “To idan Na daidaita shi Na kuma busa masa ruhina, sai ku faɗi kuna masu yi masa sujjada.”(73) Sai mala’iku dukkaninsu gaba ɗaya suka yi sujjada (74) Sai Iblisa da ya yi girman kai ya kuma zama cikin kafirai (75) (Allah) Ya ce: “Ya kai Iblisa, me ya hana ka yin sujjada ga abin da Na halitta da hannayena biyu? Ka yi girman kai ne, ko kuwa da man can ka kasance daga masu nuna isa?” (76) Sai ya ce: “Ni ai na fi shi; (domin) Ka halicce ni ne daga wuta, (shi) kuma Ka halicce shi daga taɓo.”
(77) (Sai Allah) Ya ce (da shi): “To ka fice daga cikinta (wato Aljanna) saboda kai lalle korarre ne (daga rahama)(78) “Kuma lalle la’antata tabbas ta hau kanka har zuwa ranar alƙiyama.”(79) (Sai Iblisa) ya ce: “Ya Ubangijina, Ka saurara min har zuwa ranar da za a tashe su.” (80) (Sai Allah) Ya ce: “To lalle kana cikin waɗanda za a saurara wa(81) “Har zuwa ranar lokaci sananne.”(82) Sai ya ce: “To na rantse da girmanka tabbas zan ɓatar da su baki ɗaya (83) “Sai dai bayinka waɗanda aka tsarkake daga cikinsu.”

(1) Suna nufin muminai waxanda suka riqa yi wa izgili a duniya, suna musu kallon vatattu.

قَالَ فَٱلْحَقُّ وَٱلْحَقَّ أَقُولُ ﴿٨٤﴾ لَأَمْلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنكَ وَمِمَّن تَبِعَكَ مِنْهُمْ
أَجْمَعِينَ ﴿٨٥﴾ قُلْ مَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُتَكَلِّفِينَ
﴿٨٦﴾ إِنْ هُوَ إِلَّا ذِكْرٌ لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿٨٧﴾ وَلَتَعْلَمُنَّ نَبَأَهُۥ بَعْدَ حِينٍۭ ﴿٨٨﴾

سُورَةُ الزُّمَرِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

تَنزِيلُ ٱلْكِتَٰبِ مِنَ ٱللَّهِ ٱلْعَزِيزِ ٱلْحَكِيمِ ﴿١﴾ إِنَّآ أَنزَلْنَآ إِلَيْكَ
ٱلْكِتَٰبَ بِٱلْحَقِّ فَٱعْبُدِ ٱللَّهَ مُخْلِصًا لَّهُ ٱلدِّينَ ﴿٢﴾ أَلَا
لِلَّهِ ٱلدِّينُ ٱلْخَالِصُ ۚ وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِهِۦٓ أَوْلِيَآءَ
مَا نَعْبُدُهُمْ إِلَّا لِيُقَرِّبُونَآ إِلَى ٱللَّهِ زُلْفَىٰٓ إِنَّ ٱللَّهَ يَحْكُمُ
بَيْنَهُمْ فِى مَا هُمْ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى مَنْ هُوَ
كَٰذِبٌ كَفَّارٌ ﴿٣﴾ لَّوْ أَرَادَ ٱللَّهُ أَن يَتَّخِذَ وَلَدًا لَّٱصْطَفَىٰ
مِمَّا يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ ۚ سُبْحَٰنَهُۥ ۖ هُوَ ٱللَّهُ ٱلْوَٰحِدُ ٱلْقَهَّارُ
﴿٤﴾ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ بِٱلْحَقِّ ۖ يُكَوِّرُ ٱلَّيْلَ عَلَى
ٱلنَّهَارِ وَيُكَوِّرُ ٱلنَّهَارَ عَلَى ٱلَّيْلِ ۖ وَسَخَّرَ ٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ ۖ
كُلٌّ يَجْرِى لِأَجَلٍ مُّسَمًّى ۗ أَلَا هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْغَفَّارُ ﴿٥﴾



(84) (Allah) Ya ce: “Gaskiya (daga gare Ni take), kuma gaskiyar kawai Nake faɗa!
(85) “Tabbas zan cika Jahannama da kai da kuma waɗanda suka bi ka baki ɗaya.” (86) Ka faɗa (musu): “Babu wani lada da nake tambayar ku game da shi, (wato isar da aike), kuma ni ba na cikin masu matsa wa kai (don in ƙago wani sabon saƙo)
(87) “Shi ba wani abu ba ne in ban da tunatarwa ga talikai
(88) “Kuma tabbas za ku san gaskiyar labarinsa (watau Alƙur’ani) bayan wani ɗan lokaci.”

Sura Zumar

(1) Saukar Littafi daga Allah ne Mabuwayi, Mai hikima
(2) Lalle Mu Muka saukar maka Littafi da gaskiya, to ka bauta wa Allah kana mai tsantsanta addini a gare Shi
(3) Ku saurara! Tsantsan addini na Allah ne(1). Waɗanda kuwa suka riƙi wasu majiɓinta al’amari ba Shi ba (suna cewa): “Ba ma bauta musu sai kawai don su kusanta mu ga Allah.” Lalle Allah zai yi hukunci a tsakaninsu game da abin da suke sassaɓawa a cikinsa. Lalle Allah ba Ya shiryar da wanda yake maƙaryaci, mai yawan kafirci
(4) Da Allah Ya yi nufin Ya riƙi ɗa, da sai Ya zaɓi wanda Ya ga dama daga abubuwan da Yake halitta. Tsarki ya tabbata a gare Shi. Shi ne Ɗaya, Mai rinjaye
(5) Ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya; Yana naɗa dare a kan yini, Ya kuma naɗa yini a kan dare; kuma Ya hore rana da wata; kowane yana tafiya zuwa wani lokaci ƙayyadajje. Ku saurara! Shi ne Mabuwayi, Mai yawan gafara

(1) Watau addinin kaxaita Allah da guje wa shirka.

خَلَقَكُم مِّن نَّفْسٍ وَٰحِدَةٍ ثُمَّ جَعَلَ مِنْهَا زَوْجَهَا وَأَنزَلَ لَكُم
مِّنَ ٱلْأَنْعَٰمِ ثَمَٰنِيَةَ أَزْوَٰجٍ ۚ يَخْلُقُكُمْ فِى بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمْ
خَلْقًا مِّنۢ بَعْدِ خَلْقٍ فِى ظُلُمَٰتٍ ثَلَٰثٍ ۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ لَهُ
ٱلْمُلْكُ ۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ فَأَنَّىٰ تُصْرَفُونَ ﴿٦﴾ إِن تَكْفُرُوا۟ فَإِنَّ
ٱللَّهَ غَنِىٌّ عَنكُمْ ۖ وَلَا يَرْضَىٰ لِعِبَادِهِ ٱلْكُفْرَ ۖ وَإِن تَشْكُرُوا۟ يَرْضَهُ
لَكُمْ ۗ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٌ وِزْرَ أُخْرَىٰ ۚ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُم مَّرْجِعُكُمْ
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ۚ إِنَّهُۥ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿٧﴾
* وَإِذَا مَسَّ ٱلْإِنسَٰنَ ضُرٌّ دَعَا رَبَّهُۥ مُنِيبًا إِلَيْهِ ثُمَّ إِذَا خَوَّلَهُۥ نِعْمَةً
مِّنْهُ نَسِىَ مَا كَانَ يَدْعُوٓا۟ إِلَيْهِ مِن قَبْلُ وَجَعَلَ لِلَّهِ أَندَادًا لِّيُضِلَّ
عَن سَبِيلِهِۦ ۚ قُلْ تَمَتَّعْ بِكُفْرِكَ قَلِيلًا ۖ إِنَّكَ مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلنَّارِ
﴿٨﴾ أَمَّنْ هُوَ قَٰنِتٌ ءَانَآءَ ٱلَّيْلِ سَاجِدًا وَقَآئِمًا يَحْذَرُ ٱلْءَاخِرَةَ
وَيَرْجُوا۟ رَحْمَةَ رَبِّهِۦ ۗ قُلْ هَلْ يَسْتَوِى ٱلَّذِينَ يَعْلَمُونَ وَٱلَّذِينَ
لَا يَعْلَمُونَ ۗ إِنَّمَا يَتَذَكَّرُ أُو۟لُوا۟ ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿٩﴾ قُلْ يَٰعِبَادِ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ ٱتَّقُوا۟ رَبَّكُمْ ۚ لِلَّذِينَ أَحْسَنُوا۟ فِى هَٰذِهِ ٱلدُّنْيَا حَسَنَةٌ ۗ
وَأَرْضُ ٱللَّهِ وَٰسِعَةٌ ۗ إِنَّمَا يُوَفَّى ٱلصَّٰبِرُونَ أَجْرَهُم بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴿١٠﴾

(6) Ya halicce ku daga rai guda (shi ne Adamu), sannan Ya halicci matarsa daga gare shi, Ya kuma halitta muku dangogi guda takwas na dabbobin ni'ima. Yana (shirya) halittarku a cikin cikkunan iyayenku mata, matakin halitta bayan wani matakin, cikin duffai guda uku[1]. Wannan kuwa Shi ne Allah Ubangijinku; Wanda mulki nasa ne; babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi. To ta ina ne ake juyar da ku?

(7) Idan kun kafirce, to lalle Allah Mawadaci ne ga barin ku, ba Ya kuma yarda da kafirci daga bayinsa. Idan kuwa kuka gode Zai yarda da godiyar taku. Kuma wani rai ba ya ɗaukar laifin wani. Sannan zuwa ga Ubangijinku ne makomarku take, sannan Ya ba ku labarin irin abubuwan da kuka kasance kuna aikatawa. Lalle Shi Masanin abubuwan da suke cikin ƙiraza ne

(8) Idan kuma wata cuta ta sami mutum sai ya roƙi Ubangijinsa yana mai komawa gare Shi, sannan idan Ya ba shi wata ni'ima daga gare Shi, sai ya manta abin da ya kasance yana roƙon Sa a da, ya kuma sanya abokan tarayya ga Allah don ya ɓatar (da mutane) daga hanyarsa (Allah). Ka ce: "Ka ji daɗi ɗan kaɗan da kafircinka; lalle kai kam kana daga cikin 'yan wuta."

(9) Shin yanzu wanda yake shi mai ibada ne a cikin sa'o'in dare, yana sujjada yana kuma tsayawa, yana tsoron ranar lahira yana kuma ƙaunar rahamar Ubangijinsa (zai yi daidai da wanda ba haka yake ba?) Ka ce: "Yanzu waɗanda suke da sani za su yi daidai da waɗanda ba su da sani? Ma'abota hankula ne kawai suke wa'azantuwa

(10) Ka ce[2]: "Ya ku bayina waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Ubangijinku. Waɗanda suka kyautata a wannan duniyar suna da kyakkyawan (sakamako). Kasar Allah kuma yalwatacciya ce. Lalle masu haƙuri ne kawai ake cika wa ladansu ba da lissafi ba."

(1) Watau duhun ciki da duhun mahaifa da kuma duhun mabiyiya.

(2) Allah ( ) ya umarci Manzonsa ( ) ya faxa wa bayinsa muminai a madadinsa.

قُلْ إِنِّيٓ أُمِرْتُ أَنْ أَعْبُدَ ٱللَّهَ مُخْلِصًا لَّهُ ٱلدِّينَ ﴿١١﴾ وَأُمِرْتُ لِأَنْ أَكُونَ
أَوَّلَ ٱلْمُسْلِمِينَ ﴿١٢﴾ قُلْ إِنِّيٓ أَخَافُ إِنْ عَصَيْتُ رَبِّي عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ
﴿١٣﴾ قُلِ ٱللَّهَ أَعْبُدُ مُخْلِصًا لَّهُ دِينِي ﴿١٤﴾ فَٱعْبُدُوا۟ مَا شِئْتُم مِّن دُونِهِۦ ۗ
قُلْ إِنَّ ٱلْخَٰسِرِينَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ وَأَهْلِيهِمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۗ
أَلَا ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْخُسْرَانُ ٱلْمُبِينُ ﴿١٥﴾ لَهُم مِّن فَوْقِهِمْ ظُلَلٌ مِّنَ ٱلنَّارِ
وَمِن تَحْتِهِمْ ظُلَلٌ ۚ ذَٰلِكَ يُخَوِّفُ ٱللَّهُ بِهِۦ عِبَادَهُۥ ۚ يَٰعِبَادِ فَٱتَّقُونِ ﴿١٦﴾
وَٱلَّذِينَ ٱجْتَنَبُوا۟ ٱلطَّٰغُوتَ أَن يَعْبُدُوهَا وَأَنَابُوٓا۟ إِلَى ٱللَّهِ لَهُمُ ٱلْبُشْرَىٰ ۚ
فَبَشِّرْ عِبَادِ ﴿١٧﴾ ٱلَّذِينَ يَسْتَمِعُونَ ٱلْقَوْلَ فَيَتَّبِعُونَ أَحْسَنَهُۥ ۚ
أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ هَدَىٰهُمُ ٱللَّهُ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمْ أُو۟لُوا۟ ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿١٨﴾
أَفَمَنْ حَقَّ عَلَيْهِ كَلِمَةُ ٱلْعَذَابِ أَفَأَنتَ تُنقِذُ مَن فِى ٱلنَّارِ ﴿١٩﴾
لَٰكِنِ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوْا۟ رَبَّهُمْ لَهُمْ غُرَفٌ مِّن فَوْقِهَا غُرَفٌ مَّبْنِيَّةٌ تَجْرِى
مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ ۖ وَعْدَ ٱللَّهِ لَا يُخْلِفُ ٱللَّهُ ٱلْمِيعَادَ ﴿٢٠﴾ أَلَمْ تَرَ
أَنَّ ٱللَّهَ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَسَلَكَهُۥ يَنَٰبِيعَ فِى ٱلْأَرْضِ ثُمَّ
يُخْرِجُ بِهِۦ زَرْعًا مُّخْتَلِفًا أَلْوَٰنُهُۥ ثُمَّ يَهِيجُ فَتَرَىٰهُ مُصْفَرًّا ثُمَّ
يَجْعَلُهُۥ حُطَٰمًا ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَذِكْرَىٰ لِأُو۟لِى ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿٢١﴾

(11) Ka ce: “Lalle ni an umarce ni da in bauta wa Allah ina mai tsantsanta addini gare Shi
(12) “An kuma umarce ni da in kasance farkon Musulmi.”
(13) Ka ce: “Lalle ni ina jin tsoron azabar wani yini mai girma idan na saɓi Ubangijina”
(14) Ka ce: “Allah kawai nake bauta wa, ina mai tsantsanta addinina gare Shi
(15) “Sai ku bauta wa abin da kuka ga dama ba Shi ba.” Ka ce: “Lalle asararru (su ne) waɗanda suka yi asarar rayuwarsu da ta iyalinsu ranar alƙiyama. Ku saurara!

Wannan ita ce asara bayyananniya
(16) Suna da inuwoyi na wuta a samansu, a ƙarƙashinsu kuma akwai wasu inuwoyin. Wannan ne fa Allah Yake tsoratar da bayinsa da shi. Ya ku bayina, sai ku kiyaye dokokina
(17) Waɗanda kuwa suka nisanci bautar ɗagutu[1], suka kuma koma ga Allah, suna da albishir (na Aljanna). To ka yi wa bayina aibishir
(18) Waɗanda suke sauraron magana sai su bi mafi kyawunta, waɗannan su ne waɗanda Allah Ya shiriya, kuma waɗannan su ne ma’abota hankula
(19) Yanzu wanda kalmar azaba ta tabbata a kansa (kai ne za ka iya shiyar da shi)? Yanzu kai za ka iya kuɓutar da wanda yake cikin wuta?
(20) Sai dai waɗanda suka kiyaye dokokin Ubangijinsu suna da ɗakunan benaye, a sama da su kuma akwai wasu ɗakunan benaye ginannu, ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu; (wannan) alƙawarin Allah ne; Allah ko ba Ya saɓa alƙawari
(21) Yanzu ba ka gani cewa Allah ne Ya saukar da ruwa daga sama, sannan Ya shigar da shi cikin idanuwan ruwa a ƙasa, sannan Yana fitar da shukoki masu launi iri-iri da shi, sannan ya bushe sai ka gan shi fatsi-fatsi, sannan Ya mayar da shi dudduga? Lalle a game da wannan tabbas akwai wa’azi ga ma’abota hankula

(1) Xagutu, shi ne duk wani abu da bawa ya qetare iyakar Allah ta hanyansa.

أَفَمَن شَرَحَ ٱللَّهُ صَدۡرَهُۥ لِلۡإِسۡلَٰمِ فَهُوَ عَلَىٰ نُورٖ مِّن رَّبِّهِۦۚ فَوَيۡلٞ
لِّلۡقَٰسِيَةِ قُلُوبُهُم مِّن ذِكۡرِ ٱللَّهِۚ أُوْلَٰٓئِكَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٍ ٢٢
ٱللَّهُ نَزَّلَ أَحۡسَنَ ٱلۡحَدِيثِ كِتَٰبٗا مُّتَشَٰبِهٗا مَّثَانِيَ تَقۡشَعِرُّ مِنۡهُ
جُلُودُ ٱلَّذِينَ يَخۡشَوۡنَ رَبَّهُمۡ ثُمَّ تَلِينُ جُلُودُهُمۡ وَقُلُوبُهُمۡ
إِلَىٰ ذِكۡرِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ هُدَى ٱللَّهِ يَهۡدِي بِهِۦ مَن يَشَآءُۚ وَمَن
يُضۡلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنۡ هَادٍ ٢٣ أَفَمَن يَتَّقِي بِوَجۡهِهِۦ سُوٓءَ
ٱلۡعَذَابِ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ وَقِيلَ لِلظَّٰلِمِينَ ذُوقُواْ مَا كُنتُمۡ تَكۡسِبُونَ
٢٤ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ فَأَتَىٰهُمُ ٱلۡعَذَابُ مِنۡ حَيۡثُ
لَا يَشۡعُرُونَ ٢٥ فَأَذَاقَهُمُ ٱللَّهُ ٱلۡخِزۡيَ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ وَلَعَذَابُ
ٱلۡأٓخِرَةِ أَكۡبَرُۚ لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ٢٦ وَلَقَدۡ ضَرَبۡنَا لِلنَّاسِ فِي
هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ مِن كُلِّ مَثَلٖ لَّعَلَّهُمۡ يَتَذَكَّرُونَ ٢٧ قُرۡءَانًا عَرَبِيًّا
غَيۡرَ ذِي عِوَجٖ لَّعَلَّهُمۡ يَتَّقُونَ ٢٨ ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلٗا رَّجُلٗا فِيهِ
شُرَكَآءُ مُتَشَٰكِسُونَ وَرَجُلٗا سَلَمٗا لِّرَجُلٍ هَلۡ يَسۡتَوِيَانِ مَثَلًاۚ
ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِۚ بَلۡ أَكۡثَرُهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٢٩ إِنَّكَ مَيِّتٞ وَإِنَّهُم
مَّيِّتُونَ ٣٠ ثُمَّ إِنَّكُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ عِندَ رَبِّكُمۡ تَخۡتَصِمُونَ ٣١

(22) Yanzu wanda Allah Ya buɗa masa ƙirjinsa da Musulunci don haka ya zama cikin haske daga Ubangijinsa (zai yi kamar wanda zuciyarsa ta ƙeƙashe?) To tsananin azaba ya tabbata ga masu ƙeƙasassun zukata da ba sa ambaton Allah. Waɗannan suna cikin ɓata mabayyani

(23) Allah Ya saukar da mafi kyan zance: Alƙur'ani mai kama da juna, mai biyunta (saƙo), tsikar fatun waɗanda suke tsoron Ubangijinsu suna tashi, sannan fatunsu su yi taushi, zukatansu kuwa su koma zuwa ambaton Allah. Wannan ita ce shiriyar Allah, Yana shiyar da wanda Ya ga dama da ita. Wanda kuma Allah Ya ɓatar to ba shi da mai shiryar da shi

(24) Yanzu wanda yake kare mummunar azaba da fuskarsa(1) a ranar alƙiyama (zai yi kama da wanda ba ya yi?) Aka kuma ce da azzalumai: "Ku ɗanɗani abin da kuka kasance kuna aikatawa." (25)Waɗanda suke gabaninsu sun ƙaryata, sai azaba ta zo musu daga inda ba sa tsammani

(26) Sannan Allah Ya ɗanɗana musu azabar wulaƙanci a rayuwar duniya, kuma lalle azabar lahira ta fi girma. Da sun kasance sun san (hakan)

(27) Kuma haƙiƙa Mun ba wa mutane kowane nau'i na misali a cikin wannan Alƙur'ani don su wa'azantu

(28) Alƙur'ani Balarabe marar karkata don su sami taƙawa

(29) Allah Ya ba da misali na wani namiji (bawa) wanda yake da iyayen giji masu tarayya a kansa masu jayayya (a kan ba shi umarni) da kuma wani namiiji (bawa) da ya keɓanta ga wani namiji guda, shin misalinsu za su yi daidai? Dukkan yabo ya tabbata ga Allah. A'a, yawancinsu dai ba su sani ba ne

(30) Lalle kai mai mutuwa ne, su ma kuma lalle masu mutuwa ne

(31) Sannan kuma lalle ku ɗin nan a ranar alƙiyama a wurin Ubangijinku za ku yi husuma

(1) Watau kafirin da aka xaure masa hannayensa aka kuma jefa shi wuta, don haka yake kare wuta da fuskarsa.



فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن كَذَبَ عَلَى ٱللَّهِ وَكَذَّبَ بِٱلصِّدْقِ
إِذْ جَآءَهُۥٓ ۚ أَلَيْسَ فِى جَهَنَّمَ مَثْوًى لِّلْكَٰفِرِينَ ﴿٣٢﴾ وَٱلَّذِى
جَآءَ بِٱلصِّدْقِ وَصَدَّقَ بِهِۦٓ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُتَّقُونَ ﴿٣٣﴾
لَهُم مَّا يَشَآءُونَ عِندَ رَبِّهِمْ ۚ ذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٣٤﴾
لِيُكَفِّرَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ أَسْوَأَ ٱلَّذِى عَمِلُوا۟ وَيَجْزِيَهُمْ أَجْرَهُم
بِأَحْسَنِ ٱلَّذِى كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٣٥﴾ أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِكَافٍ
عَبْدَهُۥ ۖ وَيُخَوِّفُونَكَ بِٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦ ۚ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ
فَمَا لَهُۥ مِنْ هَادٍ ﴿٣٦﴾ وَمَن يَهْدِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن مُّضِلٍّ ۗ
أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِعَزِيزٍ ذِى ٱنتِقَامٍ ﴿٣٧﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ۚ قُلْ أَفَرَءَيْتُم مَّا تَدْعُونَ
مِن دُونِ ٱللَّهِ إِنْ أَرَادَنِىَ ٱللَّهُ بِضُرٍّ هَلْ هُنَّ كَٰشِفَٰتُ
ضُرِّهِۦٓ أَوْ أَرَادَنِى بِرَحْمَةٍ هَلْ هُنَّ مُمْسِكَٰتُ رَحْمَتِهِۦ ۚ
قُلْ حَسْبِىَ ٱللَّهُ ۖ عَلَيْهِ يَتَوَكَّلُ ٱلْمُتَوَكِّلُونَ ﴿٣٨﴾ قُلْ يَٰقَوْمِ
ٱعْمَلُوا۟ عَلَىٰ مَكَانَتِكُمْ إِنِّى عَٰمِلٌ ۖ فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿٣٩﴾
مَن يَأْتِيهِ عَذَابٌ يُخْزِيهِ وَيَحِلُّ عَلَيْهِ عَذَابٌ مُّقِيمٌ ﴿٤٠﴾

(32) Wane ne ya fi zalunci fiye da wanda ya yi wa Allah karya, ya kuma karyata gaskiya lokacin da ta zo masa? Yanzu a cikin wutar Jahannama babu wurin zaman kafirai?
(33) Wanda kuwa ya zo da gaskiya ya kuma gaskata ta, waɗannan su ne masu taƙawa
(34) Suna da (sakamakon) abin da suke so daga wurin Ubangijinsu. Wannan shi ne sakamakon masu kyautatawa
(35) Don Allah Ya kankare musu mafi munin abin da suka aikata, Ya kuma saka musu ladansu da mafi kyan abin da suka kasance suna aikatawa
(36) Yanzu Allah bai ishi bawansa ba? Suna kuma tsorata ka da waɗanda suke ba Shi ba. Wanda kuwa Allah Ya ɓatar to babu wani mai shiryar da shi
(37) Wanda kuma Allah Ya shiryar da shi to babu wani mai ɓatar da shi. Yanzu Allah ba Mabuwayi ba ne, Mai ramuwar gayya?
(38) Tabbas da za ka tambaye su wanda ya halicci sammai da ƙasa, lalle za su ce: "Allah ne." Ka ce (da su): "Ku ba ni labarin waɗanda kuke bauta wa ba Allah ba, idan Allah Ya nufe ni da wata cuta, yanzu za su iya yaye cutar tasa, ko kuwa idan Ya nufe ni da rahama yanzu za su iya riƙe rahamarsa?" Ka ce: "Allah Ya ishe ni; a gare Shi ne kawai masu dogaro suke dogaro."
(39) Ka ce: "Ya ku mutanena, ku yi aiki a kan irin hanyarku, ni ma kuma zan yi aiki ne (a kan irin tawa), sannu ba da daɗewa ba za ku sani
(40) "Wanda azabar da za ta kunyata shi za ta zo masa, kuma azaba madawwamiya za ta sauka a kansa."

إِنَّآ أَنزَلْنَا عَلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ لِلنَّاسِ بِٱلْحَقِّ ۖ فَمَنِ ٱهْتَدَىٰ
فَلِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَن ضَلَّ فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيْهَا ۖ وَمَآ أَنتَ عَلَيْهِم
بِوَكِيلٍ ﴿٤١﴾ ٱللَّهُ يَتَوَفَّى ٱلْأَنفُسَ حِينَ مَوْتِهَا وَٱلَّتِى
لَمْ تَمُتْ فِى مَنَامِهَا ۖ فَيُمْسِكُ ٱلَّتِى قَضَىٰ عَلَيْهَا ٱلْمَوْتَ
وَيُرْسِلُ ٱلْأُخْرَىٰٓ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ
يَتَفَكَّرُونَ ﴿٤٢﴾ أَمِ ٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ شُفَعَآءَ ۚ قُلْ
أَوَلَوْ كَانُوا۟ لَا يَمْلِكُونَ شَيْـًٔا وَلَا يَعْقِلُونَ ﴿٤٣﴾ قُل
لِّلَّهِ ٱلشَّفَٰعَةُ جَمِيعًا ۖ لَّهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ ثُمَّ
إِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٤٤﴾ وَإِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَحْدَهُ ٱشْمَأَزَّتْ
قُلُوبُ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِٱلْءَاخِرَةِ ۖ وَإِذَا ذُكِرَ ٱلَّذِينَ مِن
دُونِهِۦٓ إِذَا هُمْ يَسْتَبْشِرُونَ ﴿٤٥﴾ قُلِ ٱللَّهُمَّ فَاطِرَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ عَٰلِمَ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ أَنتَ تَحْكُمُ بَيْنَ عِبَادِكَ
فِى مَا كَانُوا۟ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿٤٦﴾ وَلَوْ أَنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ مَا فِى
ٱلْأَرْضِ جَمِيعًا وَمِثْلَهُۥ مَعَهُۥ لَٱفْتَدَوْا۟ بِهِۦ مِن سُوٓءِ ٱلْعَذَابِ
يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۚ وَبَدَا لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مَا لَمْ يَكُونُوا۟ يَحْتَسِبُونَ ﴿٤٧﴾

(41) Lalle Mu Mun saukar maka da Littafi da gaskiya ga mutane; saboda haka duk wanda ya shiriya to ya yi wa kansa alheri, wanda kuwa ya ɓata, to lalle ya ɓata ne don kansa; kuma kai ba wakili ba ne a kansu

(42) Allah Yana karɓar rayuka lokacin mutuwarsu, da waɗanda kuma ba su mutu ba a lokacin baccinsu; sai Ya riƙe waɗanda Ya ƙaddara wa mutuwa, Ya kuma saki sauran har zuwa wani lokaci ƙayyadadde. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutane masu tunani

(43) Tabbas sun dai riƙi wasu masu ceto ne ba Allah ba. Ka ce: "Yanzu (kwa yi haka) ko da kuwa sun kasance ba sa mallakin komai, kuma ba sa hankalta?"

(44) Ka ce: "Ceto gaba ɗaya na Allah ne; mulkin sammai da ƙasa nasa ne Shi kaɗai; sannan kuma wurinsa ne kawai za a komar da ku."

(45) Idan kuma aka ambaci Allah Shi kaɗai sai zukatan waɗanda ba sa ba da gaskiya da ranar lahira su takura; idan kuwa aka ambaci waɗanda suke ba Shi ba sai ka gan su suna ta walwala

(46) Ka ce: "Ya Allah Mahaliccin sammai da ƙasa, Masanin ɓoye da sarari, Kai ne za Ka yi hukunci tsakanin bayinka game da abin da suka kasance suna yin saɓani a kansa."

(47) Da a ce waɗanda suka yi zalunci za su mallaki abin da yake bayan ƙasa baki ɗaya har da wani kamarsa a tare da shi, to da sun fanshi kansu da shi saboda munin azabar ranar lahira. Abin da kuma ba su kasance suna tsammani daga Allah ba ya bayyana a gare su

وَبَدَا لَهُمْ سَيِّـَٔاتُ مَا كَسَبُوا۟ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُوا۟ بِهِۦ
يَسْتَهْزِءُونَ ﴿٤٨﴾ فَإِذَا مَسَّ ٱلْإِنسَٰنَ ضُرٌّ دَعَانَا ثُمَّ إِذَا خَوَّلْنَٰهُ
نِعْمَةً مِّنَّا قَالَ إِنَّمَآ أُوتِيتُهُۥ عَلَىٰ عِلْمٍۭ ۚ بَلْ هِىَ فِتْنَةٌ وَلَٰكِنَّ
أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٤٩﴾ قَدْ قَالَهَا ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ فَمَآ
أَغْنَىٰ عَنْهُم مَّا كَانُوا۟ يَكْسِبُونَ ﴿٥٠﴾ فَأَصَابَهُمْ سَيِّـَٔاتُ
مَا كَسَبُوا۟ ۚ وَٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ مِنْ هَٰٓؤُلَآءِ سَيُصِيبُهُمْ سَيِّـَٔاتُ
مَا كَسَبُوا۟ وَمَا هُم بِمُعْجِزِينَ ﴿٥١﴾ أَوَلَمْ يَعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ يَبْسُطُ
ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقْدِرُ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ
﴿٥٢﴾ ۞ قُلْ يَٰعِبَادِىَ ٱلَّذِينَ أَسْرَفُوا۟ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ لَا تَقْنَطُوا۟
مِن رَّحْمَةِ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَغْفِرُ ٱلذُّنُوبَ جَمِيعًا ۚ إِنَّهُۥ هُوَ
ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٥٣﴾ وَأَنِيبُوٓا۟ إِلَىٰ رَبِّكُمْ وَأَسْلِمُوا۟ لَهُۥ مِن
قَبْلِ أَن يَأْتِيَكُمُ ٱلْعَذَابُ ثُمَّ لَا تُنصَرُونَ ﴿٥٤﴾ وَٱتَّبِعُوٓا۟ أَحْسَنَ
مَآ أُنزِلَ إِلَيْكُم مِّن رَّبِّكُم مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِيَكُمُ ٱلْعَذَابُ
بَغْتَةً وَأَنتُمْ لَا تَشْعُرُونَ ﴿٥٥﴾ أَن تَقُولَ نَفْسٌ يَٰحَسْرَتَىٰ
عَلَىٰ مَا فَرَّطتُ فِى جَنۢبِ ٱللَّهِ وَإِن كُنتُ لَمِنَ ٱلسَّٰخِرِينَ ﴿٥٦﴾

(48) Kuma munanan abubuwan da suka aikata suka bayyana a gare su, abin kuma da suka kasance suna yi wa izgili ya auka musu
(49) To idan wata cuta ta samu mutum sai ya roƙe Mu, sannan idan Mun ba shi wata ni'ima daga gare Mu sai ya ce: "Ai an ba ni ita ne kawai don sanin (cancantata)". Ba haka ba ne, ita wata jarrabawa ce kawai, sai dai yawancinsu ba sa sanin (haka)
(50) Haƙiƙa waɗanda suke gabaninsu sun faɗe ita (wannan maganar), to abin da suka kasance suna aikatawa bai wadatar da su (komai) ba
(51) Saboda haka sai (sakamakon) mummunan abin da suka aikata ya same su. Waɗanda ma suka yi zalunci daga waɗannan[1], (sakamakon) munanan abubuwan da suka aikata zai same su, kuma ba za su gagara ba
(52)Yanzu ba su sani ba ne cewa, Allah Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, Yana kuma ƙuntata wa (ga wanda ya ga dama)? Lalle a game da waɗannan tabbas akwai ayoyi ga mutane masu yin imani
(53) Ka ce[2]: "Ya ku bayina waɗanda suka ɓata kawunansu sosai (da kafirci da saɓon Allah), kada ku ɗebe ƙauna daga rahamar Allah. Lalle Allah Yana gafarta zunubai baki ɗaya[3]. Lalle Shi Mai gafara ne, Mai rahama
(54) "Ku kuma koma zuwa ga Ubangijinku, ku kuma miƙa wuya gare Shi tun gabanin azaba ta zo muku sannan ba za a taimake ku ba
(55) "Kuma ku bi mafi kyan abin da aka saukar muku daga Ubangijinku tun gabanin azaba ta zo muku ba zato ba tsammani, alhali ku ba ku sani ba
(56) "Don kada wani rai ya ce: 'Kaicona game da abin da na yi sakaci na haƙƙin Allah, ni tabbas na kasance daga masu yin izgili.'

(1) Su ne masu aikata shirka da savon Allah cikin al'ummar Annabi ( ).

(2) Allah ne yake umartar Manzonsa ( ) da ya faxa wa muminai bayin Allah.

(3) Watau ga wanda ya tuba.

أَوْ تَقُولَ لَوْ أَنَّ ٱللَّهَ هَدَىٰنِي لَكُنتُ مِنَ ٱلْمُتَّقِينَ ﴿٥٧﴾ أَوْ تَقُولَ
حِينَ تَرَى ٱلْعَذَابَ لَوْ أَنَّ لِي كَرَّةً فَأَكُونَ مِنَ ٱلْمُحْسِنِينَ
﴿٥٨﴾ بَلَىٰ قَدْ جَآءَتْكَ ءَايَٰتِي فَكَذَّبْتَ بِهَا وَٱسْتَكْبَرْتَ وَكُنتَ
مِنَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٥٩﴾ وَيَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ تَرَى ٱلَّذِينَ كَذَبُوا۟ عَلَى
ٱللَّهِ وُجُوهُهُم مُّسْوَدَّةٌ ۚ أَلَيْسَ فِى جَهَنَّمَ مَثْوًى لِّلْمُتَكَبِّرِينَ
﴿٦٠﴾ وَيُنَجِّى ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوْا۟ بِمَفَازَتِهِمْ لَا يَمَسُّهُمُ ٱلسُّوٓءُ
وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٦١﴾ ٱللَّهُ خَٰلِقُ كُلِّ شَىْءٍ ۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ
شَىْءٍ وَكِيلٌ ﴿٦٢﴾ لَّهُۥ مَقَالِيدُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۗ وَٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْخَٰسِرُونَ ﴿٦٣﴾ قُلْ
أَفَغَيْرَ ٱللَّهِ تَأْمُرُوٓنِّىٓ أَعْبُدُ أَيُّهَا ٱلْجَٰهِلُونَ ﴿٦٤﴾ وَلَقَدْ
أُوحِىَ إِلَيْكَ وَإِلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكَ لَئِنْ أَشْرَكْتَ
لَيَحْبَطَنَّ عَمَلُكَ وَلَتَكُونَنَّ مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿٦٥﴾ بَلِ
ٱللَّهَ فَٱعْبُدْ وَكُن مِّنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿٦٦﴾ وَمَا قَدَرُوا۟ ٱللَّهَ حَقَّ
قَدْرِهِۦ وَٱلْأَرْضُ جَمِيعًا قَبْضَتُهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ وَٱلسَّمَٰوَٰتُ
مَطْوِيَّٰتٌۢ بِيَمِينِهِۦ ۚ سُبْحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٦٧﴾

(57) “Ko kuma ya ce: ‘Da Allah Ya shirye ni da tabbas na kasance daga masu taƙawa.’
(58) “Ko kuma ya ce lokacin da ya ga azaba: ‘Ina ma da ina da damar komawa duniya, don in kasance daga masu kyautatawa?’”
(59) (Sai a ce da shi): “A’a, haƙiƙa ayoyina sun zo maka sai ka ƙaryata su ka kuma yi girman kai ka kasance daga kafirai.”
(60) A ranar alƙiyama kuwa za ka ga waɗanda suka yi wa Allah ƙarya fuskokinsu baƙi ƙirin. Yanzu a cikin wutar Jahannama ashe babu mazaunar masu girman kai?
(61) Allah kuma zai tserar da waɗanda suka yi taƙawa da ayyukansu, wani mummunan abu ba zai shafe su ba, kuma ba za su yi baƙin ciki ba
(62) Allah ne Mahaliccin komai; kuma Shi ne Wakili a kan komai
(63) Mabuɗan sammai da ƙasa nasa ne. Waɗanda kuwa suka kafirce wa ayoyin Allah, waɗannan su ne asararru
(64) Ka ce: “Yanzu wanin Allah kuke umarta ta da in bauta wa, ya ku waɗannan wawaye?”
(65) Haƙiƙa kuma an yi maka wahayi kai da waɗanda suka gabace ka cewa: “Tabbas idan ka yi shirka lallai aikinka zai ɓaci, kuma tabbas za ka kasance daga asararru.”
(66) A’a, Allah kaɗai za ka bauta wa, ka kuma kasance daga masu godiya
(67) Ba su kuma girmama Allah ba kamar yadda Ya cancanta a girmama Shi, alhali ƙasa ga baki ɗayanta tana cikin Damƙarsa ranar alƙiyama, sammai kuma suna nannaɗe a Hannunsa na dama. Tsarki ya tabbata a gare Shi, Ya kuma ɗaukaka game da abin da suke yin shirka (da shi)

وَنُفِخَ فِي ٱلصُّورِ فَصَعِقَ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلْأَرْضِ
إِلَّا مَن شَآءَ ٱللَّهُ ۖ ثُمَّ نُفِخَ فِيهِ أُخْرَىٰ فَإِذَا هُمْ قِيَامٌ يَنظُرُونَ
٦٨ وَأَشْرَقَتِ ٱلْأَرْضُ بِنُورِ رَبِّهَا وَوُضِعَ ٱلْكِتَٰبُ وَجِاْىٓءَ
بِٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلشُّهَدَآءِ وَقُضِيَ بَيْنَهُم بِٱلْحَقِّ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ
٦٩ وَوُفِّيَتْ كُلُّ نَفْسٍ مَّا عَمِلَتْ وَهُوَ أَعْلَمُ بِمَا يَفْعَلُونَ ٧٠
وَسِيقَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ إِلَىٰ جَهَنَّمَ زُمَرًا ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوهَا
فُتِحَتْ أَبْوَٰبُهَا وَقَالَ لَهُمْ خَزَنَتُهَآ أَلَمْ يَأْتِكُمْ رُسُلٌ مِّنكُمْ
يَتْلُونَ عَلَيْكُمْ ءَايَٰتِ رَبِّكُمْ وَيُنذِرُونَكُمْ لِقَآءَ يَوْمِكُمْ
هَٰذَا ۚ قَالُوا۟ بَلَىٰ وَلَٰكِنْ حَقَّتْ كَلِمَةُ ٱلْعَذَابِ عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ
٧١ قِيلَ ٱدْخُلُوٓا۟ أَبْوَٰبَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۖ فَبِئْسَ مَثْوَى
ٱلْمُتَكَبِّرِينَ ٧٢ وَسِيقَ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوْا۟ رَبَّهُمْ إِلَى ٱلْجَنَّةِ
زُمَرًا ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوهَا وَفُتِحَتْ أَبْوَٰبُهَا وَقَالَ لَهُمْ خَزَنَتُهَا
سَلَٰمٌ عَلَيْكُمْ طِبْتُمْ فَٱدْخُلُوهَا خَٰلِدِينَ ٧٣ وَقَالُوا۟
ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِى صَدَقَنَا وَعْدَهُۥ وَأَوْرَثَنَا ٱلْأَرْضَ
نَتَبَوَّأُ مِنَ ٱلْجَنَّةِ حَيْثُ نَشَآءُ ۖ فَنِعْمَ أَجْرُ ٱلْعَٰمِلِينَ ٧٤

(68) Aka kuma busa ƙaho, sai duk abin da yake cikin sammai da ƙasa ya halaka sai wanda Allah Ya ga dama; sannan aka sake yin wata busar, sai ga su a tsaye suna jiran tsammani

(69) Kasa kuma ta yi haske da hasken Ubangijinta, aka kuma ajiye takardu (na ayyuka), kuma aka zo da annabawa da masu shaida, kuma aka yi hukunci a tsakaninsu da gaskiya, ba kuma za a zalunce su ba

(70) Aka kuma yi wa kowane rai cikakken sakamakon abin da ya aikata, Shi ko (Allah) Yana sane da abin da suke aikatawa

(71) Aka kuma ingiza ƙeyar waɗanda suka kafirta zuwa (wutar) Jahannama ƙungiya-ƙungiya; har yayin da suka zo wurinta sai aka buɗe ƙofofinta, masu tsaronta suka ce (da su): "Yanzu manzanni daga cikinku ba su zo muku ba ne suna karanta muku ayoyin Ubangijinku, suna kuma gargaɗin ku game da haɗuwa da wannan ranar taku?" Sai suka ce: "Haka ne, (sun zo mana)," sai dai kuma kalmar azaba ta tabbata a kan kafirai."

(72) Aka ce: "Ku shiga ƙofofin Jahannama, kuna masu dawwama a cikinta;" to makomar masu girman kai ta munana

(73) Aka kuma raka waɗanda suka kiyaye dokokin Ubangijinsu zuwa Aljanna ƙungiya-ƙungiya; har yayin da suka zo wurinta, alhali an bubbuɗe ƙofofinta, kuma masu tsaronta suka ce (da su): "Aminci ya tabbata a gare ku, kun kyautata (ayyukanku), sai ku shige ta kuna masu dawwama."

(74) Suka ce: "Mun gode wa Allah Wanda Ya tabbatar mana da alƙawarinsa, Ya kuma gadar mana da ƙasa muna sauka a Aljanna a duk inda muka ga dama; to madalla da sakamakon masu aiki!"

وَتَرَى ٱلْمَلَٰٓئِكَةَ حَآفِّينَ مِنْ حَوْلِ ٱلْعَرْشِ يُسَبِّحُونَ بِحَمْدِ
رَبِّهِمْ ۚ وَقُضِىَ بَيْنَهُم بِٱلْحَقِّ ۚ وَقِيلَ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٧٥﴾

سُورَةُ غَافِرٍ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

حمٓ ﴿١﴾ تَنزِيلُ ٱلْكِتَٰبِ مِنَ ٱللَّهِ ٱلْعَزِيزِ ٱلْعَلِيمِ ﴿٢﴾ غَافِرِ ٱلذَّنۢبِ
وَقَابِلِ ٱلتَّوْبِ شَدِيدِ ٱلْعِقَابِ ذِى ٱلطَّوْلِ ۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ إِلَيْهِ
ٱلْمَصِيرُ ﴿٣﴾ مَا يُجَٰدِلُ فِىٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ فَلَا يَغْرُرْكَ
تَقَلُّبُهُمْ فِى ٱلْبِلَٰدِ ﴿٤﴾ كَذَّبَتْ قَبْلَهُمْ قَوْمُ نُوحٍ وَٱلْأَحْزَابُ
مِنۢ بَعْدِهِمْ ۖ وَهَمَّتْ كُلُّ أُمَّةٍۭ بِرَسُولِهِمْ لِيَأْخُذُوهُ ۖ
وَجَٰدَلُوا۟ بِٱلْبَٰطِلِ لِيُدْحِضُوا۟ بِهِ ٱلْحَقَّ فَأَخَذْتُهُمْ ۖ فَكَيْفَ
كَانَ عِقَابِ ﴿٥﴾ وَكَذَٰلِكَ حَقَّتْ كَلِمَتُ رَبِّكَ عَلَى ٱلَّذِينَ
كَفَرُوٓا۟ أَنَّهُمْ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ ﴿٦﴾ ٱلَّذِينَ يَحْمِلُونَ ٱلْعَرْشَ
وَمَنْ حَوْلَهُۥ يُسَبِّحُونَ بِحَمْدِ رَبِّهِمْ وَيُؤْمِنُونَ بِهِۦ وَيَسْتَغْفِرُونَ
لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ۖ رَبَّنَا وَسِعْتَ كُلَّ شَىْءٍ رَّحْمَةً وَعِلْمًا فَٱغْفِرْ
لِلَّذِينَ تَابُوا۟ وَٱتَّبَعُوا۟ سَبِيلَكَ وَقِهِمْ عَذَابَ ٱلْجَحِيمِ ﴿٧﴾

(75) Kuma za ka ga mala’iku suna kewaye da Al’arshi, suna tasbihi da yabon Ubangijnsu; aka kuma yi hukunci a tsakaninsu (halittu) da gaskiya, aka kuma ce: “Yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai.”

Sura Ghafir

(1) HA MIM
(2) Saukarwar Littafi daga Allah ne Mabuwayi, Masani
(3) Mai gafarta zunubi, Mai kuma karɓar tuba, Mai tsananin uƙuba, Mai ni’imatarwa; babu abin bauta wa da gaskiya sai Shi; makoma zuwa gare Shi ne
(4) Babu mai yin jayayya game da ayoyin Allah sai waɗanda suka kafirta, saboda haka kada yawan zirga-zirgarsu a garuruwa ya ruɗe ka
(5) Mutanen Nuhu sun ƙaryata kafin su, da kuma ƙungiyoyi (na kafirai) bayansu; kowace al’umma kuma sun yi mummunan nufi da manzonsu don su kama shi (su cutar da shi); suka kuma yi jayayya da (hujja ta) ƙarya don su rusa gaskiya da ita, sai Na kama su; to yaya uƙubata ta kasance?
(6) Kamar haka ne kuma kalmar Ubangijinka (ta azaba) ta tabbata a kan waɗanda suka kafirta cewa, lalle su ‘yan wuta ne
(7) Waɗanda suke ɗauke da Al’arshi da waɗanda suke kewaye da shi suna yin tasbihi da yabon Ubangijinsu, suna kuma yin imani da Shi, kuma suna nema wa waɗanda suka yi imani gafara, (suna cewa): “Ya Ubangiijnmu, ka yalwaci kowane abu da rahama da ilimi, to Ka gafarta wa waɗanda suka tuba suka kuma bi hanyarka, Ka kuma kiyaye su daga azabar (wutar) Jahimu

رَبَّنَا وَأَدۡخِلۡهُمۡ جَنَّٰتِ عَدۡنٍ ٱلَّتِي وَعَدتَّهُمۡ وَمَن صَلَحَ
مِنۡ ءَابَآئِهِمۡ وَأَزۡوَٰجِهِمۡ وَذُرِّيَّٰتِهِمۡۚ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَزِيزُ
ٱلۡحَكِيمُ ٨ وَقِهِمُ ٱلسَّيِّـَٔاتِۚ وَمَن تَقِ ٱلسَّيِّـَٔاتِ
يَوۡمَئِذٖ فَقَدۡ رَحِمۡتَهُۥۚ وَذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ٩ إِنَّ
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يُنَادَوۡنَ لَمَقۡتُ ٱللَّهِ أَكۡبَرُ مِن مَّقۡتِكُمۡ
أَنفُسَكُمۡ إِذۡ تُدۡعَوۡنَ إِلَى ٱلۡإِيمَٰنِ فَتَكۡفُرُونَ ١٠ قَالُواْ رَبَّنَآ
أَمَتَّنَا ٱثۡنَتَيۡنِ وَأَحۡيَيۡتَنَا ٱثۡنَتَيۡنِ فَٱعۡتَرَفۡنَا بِذُنُوبِنَا فَهَلۡ
إِلَىٰ خُرُوجٖ مِّن سَبِيلٖ ١١ ذَٰلِكُم بِأَنَّهُۥٓ إِذَا دُعِيَ ٱللَّهُ
وَحۡدَهُۥ كَفَرۡتُمۡۖ وَإِن يُشۡرَكۡ بِهِۦ تُؤۡمِنُواْۚ فَٱلۡحُكۡمُ لِلَّهِ
ٱلۡعَلِيِّ ٱلۡكَبِيرِ ١٢ هُوَ ٱلَّذِي يُرِيكُمۡ ءَايَٰتِهِۦ وَيُنَزِّلُ لَكُم مِّنَ
ٱلسَّمَآءِ رِزۡقٗاۚ وَمَا يَتَذَكَّرُ إِلَّا مَن يُنِيبُ ١٣ فَٱدۡعُواْ ٱللَّهَ
مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ وَلَوۡ كَرِهَ ٱلۡكَٰفِرُونَ ١٤ رَفِيعُ
ٱلدَّرَجَٰتِ ذُو ٱلۡعَرۡشِ يُلۡقِي ٱلرُّوحَ مِنۡ أَمۡرِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ
مِنۡ عِبَادِهِۦ لِيُنذِرَ يَوۡمَ ٱلتَّلَاقِ ١٥ يَوۡمَ هُم بَٰرِزُونَۖ لَا يَخۡفَىٰ
عَلَى ٱللَّهِ مِنۡهُمۡ شَيۡءٞۗ لِّمَنِ ٱلۡمُلۡكُ ٱلۡيَوۡمَۖ لِلَّهِ ٱلۡوَٰحِدِ ٱلۡقَهَّارِ ١٦

(8) "Ya Ubangijinmu, Ka kuma shigar da su gidajen Aljannar zama wadanda ka alkawarta musu, tare da wadanda suke salihai daga iyayensu da matayensu da kuma zuriyarsu. Lalle Kai Mabuwayi ne, Mai hikima

(9) "Ka kuma kiyaye su munanan (ayyuka). Duk kuwa wanda Ka kiyaye shi daga munanan (sakamako) a wannan rana, hakika Ka yi masa rahama. Wannan kuwa shi ne babban rabo."

(10) Lalle wadanda suka kafirta ana kiran su cewa: "Tabbas fushin Allah da ku ya fi girman fushinku ga kawunanku, lokacin da ake kiran ku zuwa imani (a duniya) sai kuke kafircewa."

(11) Suka ce: "Ya Ubangijinmu, Ka kashe mu sau biyu Ka kuma raya mu sau biyu[1], to mun amsa laifukanmu, shin ko akwai wata hanya ta fita (daga wuta)?"

(12) Wannan (sakamakon) saboda cewa, idan aka kira Allah Shi kadai sai ku kafirce, idan kuwa aka yi shirka da Shi, sai ku yi imani. To hukuncin na Allah ne Madaukaki, Mai girma


(13) Shi ne wanda Yake nuna muku ayoyinsa, Yake kuma saukar muku da arziki daga sama (watau ruwan sama). Ba kuma kowa ne yake wa'azantuwa ba sai mai komawa (ga Allah)

(14) Sai ku bauta wa Allah kuna masu tsantsanta addini gare Shi, ko da kuwa kafirai ba sa so

(15) (Shi ne) Mai madaukakan darajoji, Ma'abocin Al'arshi, Yana sauko da wahayi daga umarninsa ga wanda Ya ga dama daga bayinsa don Ya yi gargadin ranar haduwa

(16) Ranar da za su bayyana; babu wani abu nasu da zai buya ga Allah. (Zai ce): "Mulki na wane ne a yau?" (Sai Ya ce): "Na Allah Makadaici, Mai rinjaye ne."

(1) Watau ya samar da su bayan babu su, sannan ya kashe su, sannan ya sake raya su domin yi musu hisabi.


ٱلْيَوْمَ تُجْزَىٰ كُلُّ نَفْسٍۭ بِمَا كَسَبَتْ ۚ لَا ظُلْمَ ٱلْيَوْمَ ۚ إِنَّ
ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلْحِسَابِ ﴿١٧﴾ وَأَنذِرْهُمْ يَوْمَ ٱلْآزِفَةِ إِذِ ٱلْقُلُوبُ
لَدَى ٱلْحَنَاجِرِ كَٰظِمِينَ ۚ مَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنْ حَمِيمٍ وَلَا شَفِيعٍ
يُطَاعُ ﴿١٨﴾ يَعْلَمُ خَآئِنَةَ ٱلْأَعْيُنِ وَمَا تُخْفِى ٱلصُّدُورُ ﴿١٩﴾ وَٱللَّهُ
يَقْضِى بِٱلْحَقِّ ۖ وَٱلَّذِينَ يَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَقْضُونَ
بِشَىْءٍ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْبَصِيرُ ﴿٢٠﴾ ۞ أَوَلَمْ يَسِيرُوا۟ فِى
ٱلْأَرْضِ فَيَنظُرُوا۟ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ كَانُوا۟ مِن قَبْلِهِمْ ۚ
كَانُوا۟ هُمْ أَشَدَّ مِنْهُمْ قُوَّةً وَءَاثَارًا فِى ٱلْأَرْضِ فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ
بِذُنُوبِهِمْ وَمَا كَانَ لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن وَاقٍ ﴿٢١﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ
كَانَت تَّأْتِيهِمْ رُسُلُهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَكَفَرُوا۟ فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ ۚ
إِنَّهُۥ قَوِىٌّ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿٢٢﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَا
وَسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿٢٣﴾ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَهَٰمَٰنَ وَقَٰرُونَ
فَقَالُوا۟ سَٰحِرٌ كَذَّابٌ ﴿٢٤﴾ فَلَمَّا جَآءَهُم بِٱلْحَقِّ مِنْ
عِندِنَا قَالُوا۟ ٱقْتُلُوٓا۟ أَبْنَآءَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مَعَهُۥ وَٱسْتَحْيُوا۟
نِسَآءَهُمْ ۚ وَمَا كَيْدُ ٱلْكَٰفِرِينَ إِلَّا فِى ضَلَٰلٍ ﴿٢٥﴾



(17) A wannan ranar za a saka wa kowane rai da irin abin da ya aikata. Babu zalunci a wannan ranar. Lalle Allah Mai gaggawar yin hisabi ne

(18) Ka kuma tsoratar da su ranar (alkiyama) mai kusantowa, a yayin da zukata suke makare a wuyoyinsu (saboda tsananin tsoro). Azzalumai ba su da wani masoyi ko kuma wani mai ceto da za a yi wa biyayya

(19) (Allah) Yana sane da ha'incin idanuwa da kuma abin da zukata suke boyewa

(20) Allah Yana hukunci da gaskiya; wadanda kuwa suke bauta wa wanda ba Shi ba, ba sa hukunta komai. Hakika Allah Shi ne Mai ji, Mai gani

(21) Shin ba sa tafiya a bayan kasa sannan su ga yaya karshen wadanda suka kasance gabaninsu ya zama? Su sun kasance sun fi su tsananin karfi da barin gurabe na tarihi a bayan kasa, sai Allah Ya kama su da laifukansu, ba su kuma da wani mai kare su daga Allah

(22) Wannan (ya same su ne) saboda manzanninsu sun kasance suna zuwa musu da hujjoji bayyanannu, sai suka kafirce, sai Allah Ya kama su. Lalle Shi Mai (tsananin) karfi ne, Mai tsananin azaba

(23) Hakika kuma Mun aiko Musa da ayoyinmu da kuma hujja mabayyaniya

(24) Zuwa ga Fir'auna da Hamana da Karuna, sai suka ce shi mai sihiri ne, babban makaryaci

(25) To lokacin da ya zo musu da gaskiya daga wajenmu sai suka ce: "Ku kashe `ya`yan wadanda suka yi imani tare da shi, ku kuma kyale matansu da rai." Makircin kafirai bai zama ba sai a lalace

وَقَالَ فِرْعَوْنُ ذَرُونِيٓ أَقْتُلْ مُوسَىٰ وَلْيَدْعُ رَبَّهُۥٓ ۖ إِنِّيٓ أَخَافُ
أَن يُبَدِّلَ دِينَكُمْ أَوْ أَن يُظْهِرَ فِى ٱلْأَرْضِ ٱلْفَسَادَ ﴿٢٦﴾
وَقَالَ مُوسَىٰٓ إِنِّى عُذْتُ بِرَبِّى وَرَبِّكُم مِّن كُلِّ مُتَكَبِّرٍ لَّا يُؤْمِنُ
بِيَوْمِ ٱلْحِسَابِ ﴿٢٧﴾ وَقَالَ رَجُلٌ مُّؤْمِنٌ مِّنْ ءَالِ فِرْعَوْنَ
يَكْتُمُ إِيمَٰنَهُۥٓ أَتَقْتُلُونَ رَجُلًا أَن يَقُولَ رَبِّىَ ٱللَّهُ وَقَدْ
جَآءَكُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ مِن رَّبِّكُمْ ۖ وَإِن يَكُ كَٰذِبًا فَعَلَيْهِ
كَذِبُهُۥ ۖ وَإِن يَكُ صَادِقًا يُصِبْكُم بَعْضُ ٱلَّذِى يَعِدُكُمْ ۖ
إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى مَنْ هُوَ مُسْرِفٌ كَذَّابٌ ﴿٢٨﴾ يَٰقَوْمِ لَكُمُ
ٱلْمُلْكُ ٱلْيَوْمَ ظَٰهِرِينَ فِى ٱلْأَرْضِ فَمَن يَنصُرُنَا مِنۢ بَأْسِ ٱللَّهِ
إِن جَآءَنَا ۚ قَالَ فِرْعَوْنُ مَآ أُرِيكُمْ إِلَّا مَآ أَرَىٰ وَمَآ أَهْدِيكُمْ
إِلَّا سَبِيلَ ٱلرَّشَادِ ﴿٢٩﴾ وَقَالَ ٱلَّذِىٓ ءَامَنَ يَٰقَوْمِ إِنِّىٓ أَخَافُ
عَلَيْكُم مِّثْلَ يَوْمِ ٱلْأَحْزَابِ ﴿٣٠﴾ مِثْلَ دَأْبِ قَوْمِ نُوحٍ وَعَادٍ
وَثَمُودَ وَٱلَّذِينَ مِنۢ بَعْدِهِمْ ۚ وَمَا ٱللَّهُ يُرِيدُ ظُلْمًا لِّلْعِبَادِ ﴿٣١﴾
وَيَٰقَوْمِ إِنِّىٓ أَخَافُ عَلَيْكُمْ يَوْمَ ٱلتَّنَادِ ﴿٣٢﴾ يَوْمَ تُوَلُّونَ مُدْبِرِينَ
مَا لَكُم مِّنَ ٱللَّهِ مِنْ عَاصِمٍ ۗ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنْ هَادٍ ﴿٣٣﴾

(26) Fir’auna kuma ya ce: “Ku bar ni in kashe Musa, kuma (ya je) ya kirawo Ubangijin nasa; lalle ni ina jin tsoron kada ya sauya addininku ko kuma ya bayyanar da ɓarna a bayan ƙasa[1].”

(27) Musa ya ce: “Lalle ni ina neman tsari da Ubangijina, da kuma Ubangijinku daga duk wani mai girman kai da ba ya yin imani da ranar hisabi.”

(28) Kuma wani mutum mumini daga dangin Fir’auna wanda yake ɓoye imaninsa ya ce: “Yanzu kwa kashe mutum don ya ce ‘Allah ne Ubangijina’, kuma alhalin ya zo muku da hujjoji bayyanannu daga Ubangijinku? Idan ya zama maƙaryaci ne to laifin ƙaryarsa yana kansa; idan kuwa ya zama mai gaskiya, to wani abu daga abin da yake yi muku gargaɗinsa zai same ku. Lalle Allah ba Ya shiryar da wanda yake shi mai yawan ɓarna ne, maƙaryaci

(29) “Ya ku mutanena, a yau ku ne masu mulki masu ƙarfi a bayan ƙasa, to wane ne zai kare mu daga azabar Allah idan ta zo mana?” Fir’auna ya ce: “Ba abin da nake nuna muku sai abin da na gani (shi ne daidai), kuma hanyar shiriya kaɗai nake nuna muku.”

(30) Sai kuma wannan da ya yi imani ya ce: “Ya ku mutanena, lalle ni ina jiye muku tsoron irin ranar gangamin ƙungiyoyin (kafirai)

(31) “Kamar misalin al’adar mutanen Nuhu da Adawa da Samudawa da kuma waɗanda suka zo bayansu. Allah kuwa ba Ya nufin zalunci ga bayi

(32) “Kuma ya ku mutanena, lalle ni ina jiye muku tsoron ranar kiraye-kirayen juna (ranar alƙiyama)[2]

(33) “Ranar da za ku juya kuna masu ba da baya, ba ku da wani mai kare ku daga Allah. Duk kuma wanda Allah Ya ɓatar to ba shi da wani mai shiryarwa.”

(1) Watau zai kawo rikici da savani tsakanin mutane wanda zai haifar musu da yam-utsi da kashe-kashe.

(2) Watau mutane za su riqa kiran junansu saboda dangantaka ta jini suna neman alfarma.

وَلَقَدْ جَآءَكُمْ يُوسُفُ مِن قَبْلُ بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَمَا زِلْتُمْ فِى
شَكٍّ مِّمَّا جَآءَكُم بِهِۦ ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا هَلَكَ قُلْتُمْ لَن يَبْعَثَ ٱللَّهُ
مِنۢ بَعْدِهِۦ رَسُولًا ۚ كَذَٰلِكَ يُضِلُّ ٱللَّهُ مَنْ هُوَ مُسْرِفٌ
مُّرْتَابٌ ﴿٣٤﴾ ٱلَّذِينَ يُجَٰدِلُونَ فِىٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ بِغَيْرِ سُلْطَٰنٍ
أَتَىٰهُمْ ۖ كَبُرَ مَقْتًا عِندَ ٱللَّهِ وَعِندَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ۚ كَذَٰلِكَ
يَطْبَعُ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ قَلْبِ مُتَكَبِّرٍ جَبَّارٍ ﴿٣٥﴾ وَقَالَ فِرْعَوْنُ
يَٰهَٰمَٰنُ ٱبْنِ لِى صَرْحًا لَّعَلِّىٓ أَبْلُغُ ٱلْأَسْبَٰبَ ﴿٣٦﴾ أَسْبَٰبَ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ فَأَطَّلِعَ إِلَىٰٓ إِلَٰهِ مُوسَىٰ وَإِنِّى لَأَظُنُّهُۥ كَٰذِبًا ۚ
وَكَذَٰلِكَ زُيِّنَ لِفِرْعَوْنَ سُوٓءُ عَمَلِهِۦ وَصُدَّ عَنِ ٱلسَّبِيلِ ۚ
وَمَا كَيْدُ فِرْعَوْنَ إِلَّا فِى تَبَابٍ ﴿٣٧﴾ وَقَالَ ٱلَّذِىٓ ءَامَنَ
يَٰقَوْمِ ٱتَّبِعُونِ أَهْدِكُمْ سَبِيلَ ٱلرَّشَادِ ﴿٣٨﴾ يَٰقَوْمِ
إِنَّمَا هَٰذِهِ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا مَتَٰعٌ وَإِنَّ ٱلْءَاخِرَةَ هِىَ
دَارُ ٱلْقَرَارِ ﴿٣٩﴾ مَنْ عَمِلَ سَيِّئَةً فَلَا يُجْزَىٰٓ إِلَّا مِثْلَهَا ۖ
وَمَنْ عَمِلَ صَٰلِحًا مِّن ذَكَرٍ أَوْ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَأُو۟لَٰٓئِكَ
يَدْخُلُونَ ٱلْجَنَّةَ يُرْزَقُونَ فِيهَا بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴿٤٠﴾

(34) Hakika kuma Yusufu ya zo muku da (hujjoji) bayyanannu tun kafin (zuwan Musa), to ba ku gushe kuna kokwanton abin da ya zo muku da shi ba, har yayin da ya mutu sai kuka ce: “Allah ba zai sake aiko da wani manzo bayansa ba.” Kamar haka ne Allah Yake ɓatar da duk wanda shi mai ɓarna ne, mai shakka

(35) Waɗanda suke yin jayayya game da ayoyin Allah ba tare da wata hujja da ta zo musu ba; ƙyamar (wannan) a wurin Allah da wurin waɗanda suka yi imani ta girmama. Kamar haka ne Allah Yake toshe zuciyar duk wani mai girman kai, mai tsaurin rai


(36) Fir’auna kuma ya ce: “Ya Hamana, ka gina min dogon gini ko na kai ga hanyoyi

(37) “(Watau) hanyoyin (da ke kaiwa zuwa) sammai sai in gano Ubangijin Musa, lalle kuma ni ina tsammaninsa maƙaryaci ne.” Kamar haka kuma aka ƙawata wa Fir’auna mummunan aikinsa aka kuma kange shi daga hanyar (gaskiya). Makircin Fir’auna kuwa ba a komai yake ba sai cikin halaka

(38) Sai (mutumin nan) wanda ya yi imani ya ce: “Ya ku mutanena, ku bi ni in nuna muku hanyar shiriya

(39) “Ya ku mutanena, lalle wannan rayuwar ta duniya ɗan jin daɗi ne, kuma lalle lahira ita ce gidan tabbata

(40) “Wanda ya aikata wani mummunan aiki, to ba za a saka masa ba sai da kwatankwacinsa, wanda kuwa ya aikata wani kyakkyawan aiki, namiji ne ko mace alhali shi yana mumini, to waɗannan za su shiga Aljanna, a riƙa arzuta su a cikinta ba tare da lissafi ba



* وَيَٰقَوْمِ مَا لِيٓ أَدْعُوكُمْ إِلَى ٱلنَّجَوٰةِ وَتَدْعُونَنِيٓ إِلَى ٱلنَّارِ
﴿٤١﴾ تَدْعُونَنِي لِأَكْفُرَ بِٱللَّهِ وَأُشْرِكَ بِهِۦ مَا لَيْسَ لِي بِهِۦ
عِلْمٌ وَأَنَا۠ أَدْعُوكُمْ إِلَى ٱلْعَزِيزِ ٱلْغَفَّٰرِ ﴿٤٢﴾ لَا جَرَمَ أَنَّمَا
تَدْعُونَنِيٓ إِلَيْهِ لَيْسَ لَهُۥ دَعْوَةٌ فِي ٱلدُّنْيَا وَلَا فِي ٱلْءَاخِرَةِ
وَأَنَّ مَرَدَّنَآ إِلَى ٱللَّهِ وَأَنَّ ٱلْمُسْرِفِينَ هُمْ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ
﴿٤٣﴾ فَسَتَذْكُرُونَ مَآ أَقُولُ لَكُمْ ۚ وَأُفَوِّضُ أَمْرِيٓ إِلَى ٱللَّهِ ۚ
إِنَّ ٱللَّهَ بَصِيرٌۢ بِٱلْعِبَادِ ﴿٤٤﴾ فَوَقَىٰهُ ٱللَّهُ سَيِّـَٔاتِ مَا مَكَرُوا۟
وَحَاقَ بِـَٔالِ فِرْعَوْنَ سُوٓءُ ٱلْعَذَابِ ﴿٤٥﴾ ٱلنَّارُ يُعْرَضُونَ
عَلَيْهَا غُدُوًّا وَعَشِيًّا ۚ وَيَوْمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ أَدْخِلُوٓا۟ ءَالَ
فِرْعَوْنَ أَشَدَّ ٱلْعَذَابِ ﴿٤٦﴾ وَإِذْ يَتَحَآجُّونَ فِي ٱلنَّارِ
فَيَقُولُ ٱلضُّعَفَٰٓؤُا۟ لِلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُوٓا۟ إِنَّا كُنَّا لَكُمْ
تَبَعًا فَهَلْ أَنتُم مُّغْنُونَ عَنَّا نَصِيبًا مِّنَ ٱلنَّارِ ﴿٤٧﴾ قَالَ
ٱلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُوٓا۟ إِنَّا كُلٌّ فِيهَآ إِنَّ ٱللَّهَ قَدْ حَكَمَ
بَيْنَ ٱلْعِبَادِ ﴿٤٨﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ فِي ٱلنَّارِ لِخَزَنَةِ جَهَنَّمَ
ٱدْعُوا۟ رَبَّكُمْ يُخَفِّفْ عَنَّا يَوْمًا مِّنَ ٱلْعَذَابِ ﴿٤٩﴾

(41) “Kuma ya ku mutanena, me ya sa ne nake kiranku zuwa ga tsira, ku kuma kuke kira na zuwa wuta?
(42) “Kuna kira na da in kafirce wa Allah, in kuma tara Shi da abin da ba ni da wani sani a kansa, ni kuma ina kiran ku zuwa Mabuwayi, Mai yawan gafara?
(43) “Ba shakka abin da kuke kira na zuwa gare shi ba shi da wani kira karɓabbe a duniya ko a lahira, kuma lalle makomarmu zuwa ga Allah ne, maɓarnata kuma tabbas su ne ‘yan wuta
(44) “To ba da daɗewa ba za ku tuna abin da nake gaya muku. Ina kuma miƙa al’amarina zuwa ga Allah. Lalle Allah Mai ganin bayi ne.”
(45) Sai Allah Ya kiyaye shi (sakamakon) mummunan abin da suka shirya; kuma mummunar azaba ta saukar wa mutanen Fir’auna
(46) (Ita ce) wuta da za a riƙa bijirar da su a gare ta safe da yamma; Ranar tashin alƙiyama kuma za a ce: “Ku shigar da mutanen Fir’auna mafi tsananin azaba
(47) (Ka tuna) kuma lokacin da suke ta yin jayayya a cikin wuta, sai raunanan su riƙa ce wa waɗanda suka yi girman kai: “Lalle mun kasance mabiyanku (a duniya), to shin za ku iya ɗauke mana wani kaso na (azabar) wuta?”
(48) Waɗanda suka yi girman kai sai su ce: “Lalle mu duka a cikinta muke, lalle Allah Ya riga Ya yi hukunci tsakanin bayi.”
(49) Kuma waɗanda suke cikin wuta suka ce da masu tsaron Jahannama: “Ku roƙa mana Ubangijinku mana Ya saukaƙe mana azaba ta wuni (ɗaya).”

قَالُوٓاْ أَوَلَمۡ تَكُ تَأۡتِيكُمۡ رُسُلُكُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِۖ قَالُواْ بَلَىٰۚ
قَالُواْ فَٱدۡعُواْۗ وَمَا دُعَٰٓؤُاْ ٱلۡكَٰفِرِينَ إِلَّا فِي ضَلَٰلٖ ٥٠
إِنَّا لَنَنصُرُ رُسُلَنَا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا
وَيَوۡمَ يَقُومُ ٱلۡأَشۡهَٰدُ ٥١ يَوۡمَ لَا يَنفَعُ ٱلظَّٰلِمِينَ مَعۡذِرَتُهُمۡۖ
وَلَهُمُ ٱللَّعۡنَةُ وَلَهُمۡ سُوٓءُ ٱلدَّارِ ٥٢ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى
ٱلۡهُدَىٰ وَأَوۡرَثۡنَا بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱلۡكِتَٰبَ ٥٣ هُدٗى
وَذِكۡرَىٰ لِأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٥٤ فَٱصۡبِرۡ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ
حَقّٞ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لِذَنۢبِكَ وَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ رَبِّكَ بِٱلۡعَشِيِّ
وَٱلۡإِبۡكَٰرِ ٥٥ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُجَٰدِلُونَ فِيٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ
بِغَيۡرِ سُلۡطَٰنٍ أَتَىٰهُمۡ إِن فِي صُدُورِهِمۡ إِلَّا كِبۡرٞ
مَّا هُم بِبَٰلِغِيهِۚ فَٱسۡتَعِذۡ بِٱللَّهِۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ
ٱلۡبَصِيرُ ٥٦ لَخَلۡقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ أَكۡبَرُ مِنۡ
خَلۡقِ ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٥٧
وَمَا يَسۡتَوِي ٱلۡأَعۡمَىٰ وَٱلۡبَصِيرُ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَلَا ٱلۡمُسِيٓءُۚ قَلِيلٗا مَّا تَتَذَكَّرُونَ ٥٨

(50) Suka ce: “Yanzu manzanninku ba su kasance suna zo muku da (ayoyi) bayyanannu ba?” Suka ce: “Haka ne (sun zo)”. Sai su ce: “To sai ku yi ta roƙon. Roƙon kafirai kuwa bai zamo ba sai a taɓe.”

(51) Lalle Mu tabbas Muna taimakon manzanninmu da kuma waɗanda suka yi imani a rayuwar duniya da kuma ranar da shedu za su tsaya

(52) Ranar da hanzarin azzulamai ba zai amfane su ba; la’ana kuma ta tabbata a kansu, suna kuma da mummunan gida

(53) Kuma haƙiƙa Mun bai wa Musa shiriya, Muka kuwa gadar wa Banu-Isra’ila littafin (Attaura)

(54) Don shiriya da wa’azantuwa ga masu hankali

(55) Sai ka yi haƙuri, lalle alƙawarin Allah gaskiya ne, ka kuma nemi gafarar zunubinka, kuma ka yi tasbihi da yabon Ubangijinka a maraice da safiya

(56) Lalle waɗanda suke yin jayayya game da ayoyin Allah ba tare da wata hujja da ta zo musu ba, ba komai a cikin zukatansu sai neman ɗaukaka wadda ba za su same ta ba. Sai ka nemi tsari daga Allah; lalle Shi Mai ji ne, Mai gani

(57)Tabbas halittar sammai da ƙasa ta fi girma a kan halittar mutane, sai dai kuma yawancin mutane ba sa sanin (haka)

(58) Kuma makaho da mai gani ba za su yi daidai ba, kuma waɗanda suka yi imani suka yi aiki nagari ba za su yi (daidai) da mai mummunan aiki ba. Kaɗan ne ƙwarai kuke wa’azantuwa

إِنَّ ٱلسَّاعَةَ لَءَاتِيَةٌ لَّا رَيْبَ فِيهَا وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ
لَا يُؤْمِنُونَ ﴿٥٩﴾ وَقَالَ رَبُّكُمُ ٱدْعُونِيٓ أَسْتَجِبْ لَكُمْ ۚ
إِنَّ ٱلَّذِينَ يَسْتَكْبِرُونَ عَنْ عِبَادَتِي سَيَدْخُلُونَ جَهَنَّمَ
دَاخِرِينَ ﴿٦٠﴾ ٱللَّهُ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ لِتَسْكُنُوا۟
فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبْصِرًا ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ
أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَشْكُرُونَ ﴿٦١﴾ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ
خَٰلِقُ كُلِّ شَىْءٍ لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ فَأَنَّىٰ تُؤْفَكُونَ ﴿٦٢﴾
كَذَٰلِكَ يُؤْفَكُ ٱلَّذِينَ كَانُوا۟ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ يَجْحَدُونَ ﴿٦٣﴾
ٱللَّهُ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَرْضَ قَرَارًا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءً
وَصَوَّرَكُمْ فَأَحْسَنَ صُوَرَكُمْ وَرَزَقَكُم مِّنَ
ٱلطَّيِّبَٰتِ ۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ ۖ فَتَبَارَكَ ٱللَّهُ رَبُّ
ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٦٤﴾ هُوَ ٱلْحَىُّ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَٱدْعُوهُ مُخْلِصِينَ
لَهُ ٱلدِّينَ ۗ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٦٥﴾ ۞ قُلْ إِنِّى
نُهِيتُ أَنْ أَعْبُدَ ٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ لَمَّا جَآءَنِىَ
ٱلْبَيِّنَٰتُ مِن رَّبِّى وَأُمِرْتُ أَنْ أُسْلِمَ لِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٦٦﴾

(59) Lalle alkiyama tabbas za ta zo babu kokwanto a cikinta, sai dai kuma yawancin mutane ba sa yin imani

(60) Ubangijinku kuma Ya ce: "Ku roƙe Ni zan amsa muku. Lalle waɗanda suke yin girman kai game da bauta min, ba da daɗewa ba za su shiga Jahannama a wulaƙance."

(61) Allah ne wanda Ya halitta muku dare don ku natsu a cikinsa, rana kuma don ku ga (yadda za ku yi harka). Lalle Allah Mai falala ne ga mutane, sai dai kuma yawancinsu ba sa godewa

(62) Wannan Shi ne Allah Ubangijinku, Mahaliccin komai, babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi; to ina ne ake kautar da ku?

(63) Kamar haka ne ake karkatar da waɗanda suka zamanto suna musanta ayoyin Allah

(64) Allah ne wanda Ya sanya muku ƙasa ta zama wurin zama, sama kuma ta zama rufi, Ya kuma suranta ku, sai Ya kyautata surorinku, Ya kuma arzuta ku da daɗaɗan abubuwa. Wannan fa Shi ne Allah Ubangijinku. To Allah Ubangijin talikai albarkatunsa sun yawaita

(65) Shi Rayayye ne, babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, sai ku roƙe Shi kuna masu tsantsanta addini a gare Shi. Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai

(66) Ka ce: "Lalle ni an hana ni in bauta wa waɗanda kuke bauta wa ba Allah ba a yayin da (ayoyi) bayyanannu suka zo min daga Ubangijina, an kuma umarce ni da in miƙa wuya ga Ubangijin talikai

هُوَ ٱلَّذِى خَلَقَكُم مِّن تُرَابٍ ثُمَّ مِن نُّطْفَةٍ ثُمَّ مِنْ عَلَقَةٍ ثُمَّ
يُخْرِجُكُمْ طِفْلًا ثُمَّ لِتَبْلُغُوٓا۟ أَشُدَّكُمْ ثُمَّ لِتَكُونُوا۟ شُيُوخًا ۚ
وَمِنكُم مَّن يُتَوَفَّىٰ مِن قَبْلُ ۖ وَلِتَبْلُغُوٓا۟ أَجَلًا مُّسَمًّى وَلَعَلَّكُمْ
تَعْقِلُونَ ﴿٦٧﴾ هُوَ ٱلَّذِى يُحْىِۦ وَيُمِيتُ ۖ فَإِذَا قَضَىٰٓ أَمْرًا فَإِنَّمَا
يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿٦٨﴾ أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ يُجَٰدِلُونَ
فِىٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ أَنَّىٰ يُصْرَفُونَ ﴿٦٩﴾ ٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِٱلْكِتَٰبِ
وَبِمَآ أَرْسَلْنَا بِهِۦ رُسُلَنَا ۖ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ﴿٧٠﴾ إِذِ ٱلْأَغْلَٰلُ
فِىٓ أَعْنَاقِهِمْ وَٱلسَّلَٰسِلُ يُسْحَبُونَ ﴿٧١﴾ فِى ٱلْحَمِيمِ
ثُمَّ فِى ٱلنَّارِ يُسْجَرُونَ ﴿٧٢﴾ ثُمَّ قِيلَ لَهُمْ أَيْنَ مَا كُنتُمْ
تُشْرِكُونَ ﴿٧٣﴾ مِن دُونِ ٱللَّهِ ۖ قَالُوا۟ ضَلُّوا۟ عَنَّا بَل لَّمْ نَكُن
نَّدْعُوا۟ مِن قَبْلُ شَيْـًٔا ۚ كَذَٰلِكَ يُضِلُّ ٱللَّهُ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٧٤﴾
ذَٰلِكُم بِمَا كُنتُمْ تَفْرَحُونَ فِى ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ وَبِمَا كُنتُمْ
تَمْرَحُونَ ﴿٧٥﴾ ٱدْخُلُوٓا۟ أَبْوَٰبَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۖ فَبِئْسَ مَثْوَى
ٱلْمُتَكَبِّرِينَ ﴿٧٦﴾ فَٱصْبِرْ إِنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ ۖ فَإِمَّا نُرِيَنَّكَ
بَعْضَ ٱلَّذِى نَعِدُهُمْ أَوْ نَتَوَفَّيَنَّكَ فَإِلَيْنَا يُرْجَعُونَ ﴿٧٧﴾



(67) “Shi ne wanda Ya halicce ku daga ƙasa, sannan daga ɗigon maniyyi, sannan daga gudan jini, daga nan Ya fito da ku kuna jarirai, sannan don ku kai ƙarfinku, sannan kuma ku zama tsofaffi. Daga cikinku kuma akwai wanda ake karɓar ransa kafin wannan; don kuma ku isa zuwa wani lokaci ƙayyadajje[1], don kuma ku hankalta

(68) “Shi ne wanda Yake rayawa Yake kuma kashewa; to idan zai hukunta wani al’amari sai kawai Ya ce da shi: ‘Kasance’, sai ya kasance.”

(69) Ba ka ganin waɗanda suke jayayya game da ayoyin Allah, to ta yaya ake kautar da su?

(70) (Su ne) waɗanda suka ƙaryata Alƙur’ani da kuma abin da Muka aiko manzanninmu da shi; to ba da daɗewa ba za su sani

(71) (Su ne) waɗanda suka ƙaryata Alƙur’ani da kuma abin da Muka aiko manzanninmu da shi; to ba da daɗewa ba za su sani

(72) A cikin tafasasshen ruwan, sannan kuma ana ƙona su a cikin wuta

(73) Sannan kuma a ce da su: “Ina abin da kuka kasance kuna shirka da shi?

(74) “Wanda ba Allah ba?” Suka ce: “Sun ɓace mana; ai ba mu kasance muna bauta wa wani abu ba a da”. Kamar haka ne Allah Yake ɓatar da kafirai

(75) Wannan fa (ya same ku ne) saboda abin da kuka kasance kuna yin girman kai da shi a bayan ƙasa ba da wata hujja ba, da kuma abin da kuka kasance kuna yin walwala da shi

(76) (Za a ce da su): “Ku shiga ƙofofin Jahannama kuna masu dawwama a cikinta”; to makomar masu girman kai ta munana

(77) Sai ka yi haƙuri, lalle alƙawarin Allah gaskiya ne. To idan Mun nuna maka sashin abin da Muke yi musu alƙawari da shi na narko; ko kuma Mun karɓi ranka, to zuwa gare Mu dai za a dawo da su

(1) Wanda ba za su rage ba ba kuma za su qara ba, watau lokacin mutuwarsu.

وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلًا مِّن قَبْلِكَ مِنْهُم مَّن قَصَصْنَا عَلَيْكَ
وَمِنْهُم مَّن لَّمْ نَقْصُصْ عَلَيْكَ ۗ وَمَا كَانَ لِرَسُولٍ أَن يَأْتِيَ
بِآيَةٍ إِلَّا بِإِذْنِ اللَّهِ ۚ فَإِذَا جَاءَ أَمْرُ اللَّهِ قُضِيَ بِالْحَقِّ وَخَسِرَ
هُنَالِكَ الْمُبْطِلُونَ ﴿٧٨﴾ اللَّهُ الَّذِي جَعَلَ لَكُمُ الْأَنْعَامَ
لِتَرْكَبُوا مِنْهَا وَمِنْهَا تَأْكُلُونَ ﴿٧٩﴾ وَلَكُمْ فِيهَا مَنَافِعُ
وَلِتَبْلُغُوا عَلَيْهَا حَاجَةً فِي صُدُورِكُمْ وَعَلَيْهَا وَعَلَى
الْفُلْكِ تُحْمَلُونَ ﴿٨٠﴾ وَيُرِيكُمْ آيَاتِهِ ۖ فَأَيَّ آيَاتِ اللَّهِ
تُنكِرُونَ ﴿٨١﴾ أَفَلَمْ يَسِيرُوا فِي الْأَرْضِ فَيَنظُرُوا كَيْفَ
كَانَ عَاقِبَةُ الَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ ۚ كَانُوا أَكْثَرَ مِنْهُمْ وَأَشَدَّ
قُوَّةً وَآثَارًا فِي الْأَرْضِ فَمَا أَغْنَىٰ عَنْهُم مَّا كَانُوا يَكْسِبُونَ
﴿٨٢﴾ فَلَمَّا جَاءَتْهُمْ رُسُلُهُم بِالْبَيِّنَاتِ فَرِحُوا بِمَا عِندَهُم مِّنَ
الْعِلْمِ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُوا بِهِ يَسْتَهْزِئُونَ ﴿٨٣﴾ فَلَمَّا رَأَوْا
بَأْسَنَا قَالُوا آمَنَّا بِاللَّهِ وَحْدَهُ وَكَفَرْنَا بِمَا كُنَّا بِهِ
مُشْرِكِينَ ﴿٨٤﴾ فَلَمْ يَكُ يَنفَعُهُمْ إِيمَانُهُمْ لَمَّا رَأَوْا بَأْسَنَا ۖ سُنَّتَ
اللَّهِ الَّتِي قَدْ خَلَتْ فِي عِبَادِهِ ۖ وَخَسِرَ هُنَالِكَ الْكَافِرُونَ ﴿٨٥﴾

(78) Hakika Mun aiko manzanni a gabaninka, daga cikinsu akwai wadanda Muka labarta maka akwai kuma daga cikinsu wadanda ba Mu labarta maka ba. Ba zai yiwu ba ga wani manzo ya zo da wata aya sai da izinin Allah. Sannan idan al'amarin Allah ya zo, to sai a yi hukunci da gaskiya, kuma a nan ne mabarnata za su yi asara

(79) Allah ne wanda Ya halitta muku dabbobin ni'ima don ku hau wasu daga cikinsu, kuma daga cikinsu kuke ci

(80) Kuna kuma da wasu abubuwan amfani game da su, don kuma ku isa (wurin) da kuke da bukatar isa a cikin zukatanku a kansu, kuma a kansu ne da kuma a kan jiragen ruwa ake daukar ku


(81) Yana kuma nuna muku ayoyinsa, to wacce (aya) ce (daga) ayoyin Allah kuke musawa?

(82) Shin ba za su yi tafiya ba a bayan kasa sannan su duba yadda karshen wadanda suke gabaninsu ya zama? Sun zamanto sun fi su yawa, sun kuma fi su tsananin karfi da barin gurabe a bayan kasa; to abin da suka kasance suna aikatawa bai wadatar musu da komai ba

(83) Sannan lokacin da manzanninsu suka zo musu da (ayoyi) bayyanannu, sai suka nuna farin ciki da ilimin da ke gare su, abin kuma da suka kasance suna yi wa izgili ya saukar musu

(84) To lokacin da suka ga azabarmu sai suka ce: "Mun yi imani da Allah Shi kadai, mun kuma kafirce wa abin da muka kasance muna yin shirka da shi."

(85) To imaninsu bai zamanto zai amfane su ba yayin da suka ga azabarmu; wannan sunna ce ta Allah wadda ta shude a kan bayinsa. Kafirai kuma sun yi asara a nan


سُورَةُ فُصِّلَتْ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حمٓ ﴿١﴾ تَنزِيلٌ مِّنَ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ ﴿٢﴾ كِتَابٌ فُصِّلَتْ آيَاتُهُ
قُرْآنًا عَرَبِيًّا لِّقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ﴿٣﴾ بَشِيرًا وَنَذِيرًا فَأَعْرَضَ أَكْثَرُهُمْ
فَهُمْ لَا يَسْمَعُونَ ﴿٤﴾ وَقَالُوا قُلُوبُنَا فِي أَكِنَّةٍ مِّمَّا تَدْعُونَا إِلَيْهِ
وَفِي آذَانِنَا وَقْرٌ وَمِن بَيْنِنَا وَبَيْنِكَ حِجَابٌ فَاعْمَلْ إِنَّنَا عَامِلُونَ
﴿٥﴾ قُلْ إِنَّمَا أَنَا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ يُوحَىٰ إِلَيَّ أَنَّمَا إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَاحِدٌ
فَاسْتَقِيمُوا إِلَيْهِ وَاسْتَغْفِرُوهُ ۗ وَوَيْلٌ لِّلْمُشْرِكِينَ ﴿٦﴾ الَّذِينَ
لَا يُؤْتُونَ الزَّكَاةَ وَهُم بِالْآخِرَةِ هُمْ كَافِرُونَ ﴿٧﴾ إِنَّ الَّذِينَ
آمَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ لَهُمْ أَجْرٌ غَيْرُ مَمْنُونٍ ﴿٨﴾ * قُلْ أَئِنَّكُمْ
لَتَكْفُرُونَ بِالَّذِي خَلَقَ الْأَرْضَ فِي يَوْمَيْنِ وَتَجْعَلُونَ لَهُ أَندَادًا ۚ
ذَٰلِكَ رَبُّ الْعَالَمِينَ ﴿٩﴾ وَجَعَلَ فِيهَا رَوَاسِيَ مِن فَوْقِهَا
وَبَارَكَ فِيهَا وَقَدَّرَ فِيهَا أَقْوَاتَهَا فِي أَرْبَعَةِ أَيَّامٍ سَوَاءً
لِّلسَّائِلِينَ ﴿١٠﴾ ثُمَّ اسْتَوَىٰ إِلَى السَّمَاءِ وَهِيَ دُخَانٌ فَقَالَ
لَهَا وَلِلْأَرْضِ ائْتِيَا طَوْعًا أَوْ كَرْهًا قَالَتَا أَتَيْنَا طَائِعِينَ ﴿١١﴾

Sura Fussilat

(1) HA MIM[1] .
(2) (Alkur'ani) saukakke ne daga (Allah) Mai rahama, Mai jin kai
(3) (Shi) Littafi ne Alkur'ani Balarabe da aka rarrabe ayoyinsa ga mutanen da suke sanin (ma'anarsa)
(4) Mai albishir ne kuma mai gargadi, sai yawancinsu suka bijire, don haka su ba sa jin (kira)
(5) Suka kuma ce: "Zukatanmu suna cikin rufi game da abin da kuke kiran mu zuwa gare shi; a cikin kunnuwanmu kuma akwai nauyi[2], kuma tsakaninmu da kai akwai shamaki[3], sai ka yi aiki da (addininka), lalle mu ma masu yin aiki ne (da namu)."
(6) Ka ce: "Ni ba wani ba ne sai mutum kamarku, ana yiwo min wahayin cewa, abin bautarku abin bauta ne Guda Daya, sai ku miƙe kyam zuwa gare Shi, kuma ku nemi gafararsa. Tsananin azaba kuma ya tabbata ga mushirikai
(7) "Waɗanda ba sa ba da zakka, kuma su masu kafircewa ne da (ranar) lahira."
(8) Lalle waɗanda suka yi imani kuma suka yi aiki nagari suna da lada marar yankewa
(9) Ka ce: "Yanzu kwa riƙa kafircewa da wanda Ya halicci ƙasa a cikin (gwargwadon) kwana biyu, kuna kuma sanya masa kishiyoyi? Wannan fa Shi ne Ubangijin talikai!
(10) "Ya kuma sanya kafaffun duwatsu a cikinta daga samanta, Ya kuma yi albarka a cikinta, Ya kuma ƙaddara dangogin abincinta a cikin kwana huɗu (tare da kwanaki biyu na halittar ƙasa) daidai da daidai ga masu tambaya.
(11) "Sannan Ya nufi zuwa sama, (a sannan) ita kuma hayaki ce, sai Ya ce da ita da kuma ƙasa: "Ku zo cikin biyayya ko kuma bisa tilas." Suka ce: 'Mun zo muna masu biyayya'

(1) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Watau akwai kurumta tare da kunnuwansu, don haka ba sa jin duk wani kira da ake yi musu.

(3) Wanda yake hana muryarsa isa zuwa inda suke.

فَقَضَىٰهُنَّ سَبۡعَ سَمَٰوَاتٖ فِي يَوۡمَيۡنِ وَأَوۡحَىٰ فِي كُلِّ سَمَآءٍ أَمۡرَهَاۚ
وَزَيَّنَّا ٱلسَّمَآءَ ٱلدُّنۡيَا بِمَصَٰبِيحَ وَحِفۡظٗاۚ ذَٰلِكَ تَقۡدِيرُ ٱلۡعَزِيزِ
ٱلۡعَلِيمِ ١٢ فَإِنۡ أَعۡرَضُواْ فَقُلۡ أَنذَرۡتُكُمۡ صَٰعِقَةٗ مِّثۡلَ صَٰعِقَةِ
عَادٖ وَثَمُودَ ١٣ إِذۡ جَآءَتۡهُمُ ٱلرُّسُلُ مِنۢ بَيۡنِ أَيۡدِيهِمۡ وَمِنۡ
خَلۡفِهِمۡ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّا ٱللَّهَۖ قَالُواْ لَوۡ شَآءَ رَبُّنَا لَأَنزَلَ مَلَٰٓئِكَةٗ
فَإِنَّا بِمَآ أُرۡسِلۡتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ ١٤ فَأَمَّا عَادٞ فَٱسۡتَكۡبَرُواْ فِي
ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَقَالُواْ مَنۡ أَشَدُّ مِنَّا قُوَّةًۖ أَوَلَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّ ٱللَّهَ
ٱلَّذِي خَلَقَهُمۡ هُوَ أَشَدُّ مِنۡهُمۡ قُوَّةٗۖ وَكَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَجۡحَدُونَ
١٥ فَأَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمۡ رِيحٗا صَرۡصَرٗا فِيٓ أَيَّامٖ نَّحِسَاتٖ لِّنُذِيقَهُمۡ
عَذَابَ ٱلۡخِزۡيِ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ وَلَعَذَابُ ٱلۡأٓخِرَةِ أَخۡزَىٰۖ وَهُمۡ
لَا يُنصَرُونَ ١٦ وَأَمَّا ثَمُودُ فَهَدَيۡنَٰهُمۡ فَٱسۡتَحَبُّواْ ٱلۡعَمَىٰ عَلَى
ٱلۡهُدَىٰ فَأَخَذَتۡهُمۡ صَٰعِقَةُ ٱلۡعَذَابِ ٱلۡهُونِ بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ
١٧ وَنَجَّيۡنَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَكَانُواْ يَتَّقُونَ ١٨ وَيَوۡمَ يُحۡشَرُ أَعۡدَآءُ ٱللَّهِ
إِلَى ٱلنَّارِ فَهُمۡ يُوزَعُونَ ١٩ حَتَّىٰٓ إِذَا مَا جَآءُوهَا شَهِدَ عَلَيۡهِمۡ
سَمۡعُهُمۡ وَأَبۡصَٰرُهُمۡ وَجُلُودُهُم بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٢٠

(12) “Sai Ya mayar da su sammai bakwai a cikin kwana biyu, Ya kuma yi wa kowacce sama wahayin umarninta. Muka kuma ƙawata saman duniya da taurari da kuma tsaro[1]. Wannan tsari ne na Allah Mabuwayi, Masani.”
(13) To idan suka bijire sai ka ce: “Na tsoratar da ku da tsawa irin tsawar Adawa da Samudawa
(14) “Lokacin da manzanninsu suka zo musu ta gabansu da ta bayansu[2] cewa: ‘Kada ku bauta wa komai sai Allah.’” Suka ce: “Da Ubangijinmu Ya ga dama, da Ya saukar da mala’iku, saboda haka mu lalle masu kafirce wa abin da aka aiko ku da shi ne.’”
(15) Amma Adawa sai suka yi girman kai a bayan ƙasa ba a kan gaskiya ba, suka kuma ce: “Wane ne ya fi mu tsananin ƙarfi?” Yanzu ba su ga cewa lalle Allah wanda Ya halicce su Ya fi su tsananin ƙarfi ba? Sun kuma kasance suna musanta ayoyinmu
(16) Sai Muka aiko musu da wata iska mai ƙara a wasu kwanaki masu cike da shu’umci don Mu ɗanɗana musu azabar kunyata a rayuwar duniya; azabar lahira kuma ta fi kunyatarwa; alhalin su ba za a taimake su ba
(17) Amma Samudawa kuma sai Muka nuna musu hanyar shiriya, sai suka zaɓi ɓata a kan shiriya, sai tsawar azabar wulaƙanci ta kama su saboda abin da suka kasance suna tsuwurwuta
(18) Muka kuma tserar da waɗanda suka yi imani suka kuma kasance masu kiyaye dokokin Allah
(19) (Ka tuna) kuma ranar da za a tara maƙiya Allah zuwa wuta ana kuma kora su
(20) Har sai lokacin da suka zo mata, jinsu da ganinsu da fatunsu za su ba da shaida a kan abin da suka kasance suna aikatawa

(1) Watau daga aljannu masu qoqarin satar sauraro.

(2) Watau suka yi amfani da hanyoyi daban-daban domin isar musu da saqon Allah

وَقَالُوا۟ لِجُلُودِهِمْ لِمَ شَهِدتُّمْ عَلَيْنَا ۖ قَالُوٓا۟ أَنطَقَنَا ٱللَّهُ ٱلَّذِىٓ
أَنطَقَ كُلَّ شَىْءٍ وَهُوَ خَلَقَكُمْ أَوَّلَ مَرَّةٍ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٢١﴾
وَمَا كُنتُمْ تَسْتَتِرُونَ أَن يَشْهَدَ عَلَيْكُمْ سَمْعُكُمْ وَلَآ أَبْصَٰرُكُمْ
وَلَا جُلُودُكُمْ وَلَٰكِن ظَنَنتُمْ أَنَّ ٱللَّهَ لَا يَعْلَمُ كَثِيرًا مِّمَّا تَعْمَلُونَ
﴿٢٢﴾ وَذَٰلِكُمْ ظَنُّكُمُ ٱلَّذِى ظَنَنتُم بِرَبِّكُمْ أَرْدَىٰكُمْ فَأَصْبَحْتُم
مِّنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿٢٣﴾ فَإِن يَصْبِرُوا۟ فَٱلنَّارُ مَثْوًى لَّهُمْ ۖ وَإِن يَسْتَعْتِبُوا۟
فَمَا هُم مِّنَ ٱلْمُعْتَبِينَ ﴿٢٤﴾ ۞ وَقَيَّضْنَا لَهُمْ قُرَنَآءَ فَزَيَّنُوا۟ لَهُم
مَّا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ وَحَقَّ عَلَيْهِمُ ٱلْقَوْلُ فِىٓ أُمَمٍ قَدْ
خَلَتْ مِن قَبْلِهِم مِّنَ ٱلْجِنِّ وَٱلْإِنسِ ۖ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ خَٰسِرِينَ ﴿٢٥﴾
وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لَا تَسْمَعُوا۟ لِهَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ وَٱلْغَوْا۟ فِيهِ
لَعَلَّكُمْ تَغْلِبُونَ ﴿٢٦﴾ فَلَنُذِيقَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ عَذَابًا شَدِيدًا
وَلَنَجْزِيَنَّهُمْ أَسْوَأَ ٱلَّذِى كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٢٧﴾ ذَٰلِكَ جَزَآءُ أَعْدَآءِ ٱللَّهِ
ٱلنَّارُ ۖ لَهُمْ فِيهَا دَارُ ٱلْخُلْدِ جَزَآءًۢ بِمَا كَانُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا يَجْحَدُونَ
﴿٢٨﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ رَبَّنَآ أَرِنَا ٱلَّذَيْنِ أَضَلَّانَا مِنَ ٱلْجِنِّ
وَٱلْإِنسِ نَجْعَلْهُمَا تَحْتَ أَقْدَامِنَا لِيَكُونَا مِنَ ٱلْأَسْفَلِينَ ﴿٢٩﴾

(21) Sai Suka ce da fatunsu: "Don me kuka ba da shaida a kanmu?" Suka ce: "Allah da Ya bai wa kowane abu ikon yin furuci mu ma Shi Ya ba mu ikon furuci, Shi ne kuma Ya halicce ku tun farko, gare Shi kuma kaɗai za a mayar da ku."
(22) Kuma ba ku kasance kuna ɓoye (ayyukanku) ba, don gudun kada jinku da ganinku da fatunku su ba da shaida a kanku ba, sai dai kuna tsammanin cewa Allah ba Ya sane da yawancin abin da kuke aikatawa
(23) Wannan kuma shi ne zatonku da kuka yi ga Ubangijinku da ya hallakar da ku, sai kuka wayi gari cikin hasararru
(24) To idan ma sun yi haƙuri wuta ce dai makomarsu; idan kuma suka nemi kawo wani hanzari, to su ba sa cikin waɗanda za a karɓi hanzarinsu
(25) Muka kuma haɗa su da abokai (shaiɗanu), sai suka ƙawata musu abin da yake gabansu (na duniya) da abin da yake bayansu (na musun alƙiyama), sai kalmar (azaba) ta tabbata a kansu (na zamantowa) cikin al'ummun da suka gabace su na aljannu da mutane; lalle su, sun kasance hasararru
(26) Waɗanda kuma suka kafirta suka ce: "Kada ku saurari wannan Alƙur'ani, ku riƙa yin hayaniya a cikinsa(1) don ku yi rinjaye."
(27) To tabbas za Mu ɗanɗana wa waɗanda suka kafirta azaba mai tsanani, kuma tabbas za mu saka musu da mafi munin abin da suka kasance suna aikatawa
(28) Wannan fa shi ne sakamakon maƙiya Allah (watau) wuta; suna da gidan dawwama a cikinta; sakamako ne saboda abin da suka kasance suna musuntawa na ayoyinmu
(29) Waɗanda kuma suka kafirta suka ce: "Ya Ubangijinmu, Ka nuna mana waɗanda suka ɓatar da mu daga aljannu da mutane, mu sanya su a ƙarƙashin dugaduganmu don su zamanto cikin na can ƙasan ƙasa."

(1) Watau ku riqa hayaniya da hargowa duk sanda ake karanta shi domin kada mutane su ji abin da ake faxa.

إِنَّ ٱلَّذِينَ قَالُوا۟ رَبُّنَا ٱللَّهُ ثُمَّ ٱسْتَقَٰمُوا۟ تَتَنَزَّلُ عَلَيْهِمُ
ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ أَلَّا تَخَافُوا۟ وَلَا تَحْزَنُوا۟ وَأَبْشِرُوا۟ بِٱلْجَنَّةِ
ٱلَّتِى كُنتُمْ تُوعَدُونَ ﴿٣٠﴾ نَحْنُ أَوْلِيَآؤُكُمْ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا
وَفِى ٱلْءَاخِرَةِ ۖ وَلَكُمْ فِيهَا مَا تَشْتَهِىٓ أَنفُسُكُمْ وَلَكُمْ
فِيهَا مَا تَدَّعُونَ ﴿٣١﴾ نُزُلًا مِّنْ غَفُورٍ رَّحِيمٍ ﴿٣٢﴾ وَمَنْ أَحْسَنُ
قَوْلًا مِّمَّن دَعَآ إِلَى ٱللَّهِ وَعَمِلَ صَٰلِحًا وَقَالَ إِنَّنِى مِنَ
ٱلْمُسْلِمِينَ ﴿٣٣﴾ وَلَا تَسْتَوِى ٱلْحَسَنَةُ وَلَا ٱلسَّيِّئَةُ ۚ ٱدْفَعْ
بِٱلَّتِى هِىَ أَحْسَنُ فَإِذَا ٱلَّذِى بَيْنَكَ وَبَيْنَهُۥ عَدَٰوَةٌ كَأَنَّهُۥ
وَلِىٌّ حَمِيمٌ ﴿٣٤﴾ وَمَا يُلَقَّىٰهَآ إِلَّا ٱلَّذِينَ صَبَرُوا۟ وَمَا يُلَقَّىٰهَآ
إِلَّا ذُو حَظٍّ عَظِيمٍ ﴿٣٥﴾ وَإِمَّا يَنزَغَنَّكَ مِنَ ٱلشَّيْطَٰنِ نَزْغٌ
فَٱسْتَعِذْ بِٱللَّهِ ۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٣٦﴾ وَمِنْ ءَايَٰتِهِ
ٱلَّيْلُ وَٱلنَّهَارُ وَٱلشَّمْسُ وَٱلْقَمَرُ ۚ لَا تَسْجُدُوا۟ لِلشَّمْسِ
وَلَا لِلْقَمَرِ وَٱسْجُدُوا۟ لِلَّهِ ٱلَّذِى خَلَقَهُنَّ إِن كُنتُمْ
إِيَّاهُ تَعْبُدُونَ ﴿٣٧﴾ فَإِنِ ٱسْتَكْبَرُوا۟ فَٱلَّذِينَ عِندَ
رَبِّكَ يُسَبِّحُونَ لَهُۥ بِٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ وَهُمْ لَا يَسْـَٔمُونَ ﴿٣٨﴾ ۩

(30) Lalle waɗanda suka ce: “Allah ne Ubangijinmu”, sannan suka tsaya kyam, to mala’iku za su sauko musu (lokacin mutuwa suna cewa): “Kada ku tsorata, kuma kada ku yi baƙin ciki, kuma ku yi farin ciki da Aljanna wadda kuka kasance ana yi muku alƙawarinta

(31) “Mu masoyanku ne a rayuwar duniya da kuma ta lahira; kuma a cikinta (Aljanna) za ku sami duk abin da rayukanku suke marmari, za kuma ku sami duk abin da kuke nema a cikinta

(32) “Liyafa ce daga (Allah) Mai gafara, Mai jin ƙai.”

(33) Wane ne ya fi kyakkyawar magana fiye da wanda ya yi kira zuwa ga Allah ya kuma yi aiki nagari, kuma ya ce: “Lalle ni ina daga cikin Musulmi?”

(34) Kyakkyawan (abu) da mummuna ba za su zama ɗaya ba. To ka ture mummuna da abin da ya fi kyau, to sai ka ga wanda yake tsakaninsa da kai gaba ce, ya zamanto kamar wani masoyi ne na ƙut da ƙut

(35) Ba kowa ake bai wa wannan kyakkyawar ɗabi’ar ba sai waɗanda suka yi haƙuri, ba kowa ake bai wa ita ba sai mai babban rabo

(36) Idan kuma wani tunzuri daga Shaiɗan ya tunzura ka, to sai ka nemi tsari daga Allah; lalle Shi Mai ji ne, Masani

(37) Kuma dare da wuni da rana da wata suna daga ayoyinsa. Kada ku yi sujjada ga rana ko ga wata, ku yi sujjada ga Allah Wanda Ya halicce su idan har kun kasance Shi kaɗai kuke bauta wa

(38) Idan kuwa sun yi girman kai, to waɗanda suke wurin Ubangijinka (mala’iku) suna yi masa tasbihi dare da rana, kuma su ba sa ƙosawa

وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنَّكَ تَرَى ٱلْأَرْضَ خَٰشِعَةً فَإِذَآ أَنزَلْنَا عَلَيْهَا ٱلْمَآءَ
ٱهْتَزَّتْ وَرَبَتْ ۚ إِنَّ ٱلَّذِىٓ أَحْيَاهَا لَمُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰٓ ۚ إِنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ
قَدِيرٌ ﴿٣٩﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُلْحِدُونَ فِىٓ ءَايَٰتِنَا لَا يَخْفَوْنَ عَلَيْنَا ۗ أَفَمَن
يُلْقَىٰ فِى ٱلنَّارِ خَيْرٌ أَم مَّن يَأْتِىٓ ءَامِنًا يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۚ ٱعْمَلُوا۟ مَا شِئْتُمْ
إِنَّهُۥ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿٤٠﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِٱلذِّكْرِ لَمَّا جَآءَهُمْ ۖ
وَإِنَّهُۥ لَكِتَٰبٌ عَزِيزٌ ﴿٤١﴾ لَّا يَأْتِيهِ ٱلْبَٰطِلُ مِنۢ بَيْنِ يَدَيْهِ وَلَا مِنْ
خَلْفِهِۦ ۖ تَنزِيلٌ مِّنْ حَكِيمٍ حَمِيدٍ ﴿٤٢﴾ مَّا يُقَالُ لَكَ إِلَّا مَا قَدْ قِيلَ
لِلرُّسُلِ مِن قَبْلِكَ ۚ إِنَّ رَبَّكَ لَذُو مَغْفِرَةٍ وَذُو عِقَابٍ أَلِيمٍ
﴿٤٣﴾ وَلَوْ جَعَلْنَٰهُ قُرْءَانًا أَعْجَمِيًّا لَّقَالُوا۟ لَوْلَا فُصِّلَتْ ءَايَٰتُهُۥٓ ۖ
ءَا۬عْجَمِىٌّ وَعَرَبِىٌّ ۗ قُلْ هُوَ لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ هُدًى وَشِفَآءٌ ۖ وَٱلَّذِينَ
لَا يُؤْمِنُونَ فِىٓ ءَاذَانِهِمْ وَقْرٌ وَهُوَ عَلَيْهِمْ عَمًى ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ
يُنَادَوْنَ مِن مَّكَانٍۭ بَعِيدٍ ﴿٤٤﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ
فَٱخْتُلِفَ فِيهِ ۚ وَلَوْلَا كَلِمَةٌ سَبَقَتْ مِن رَّبِّكَ لَقُضِىَ
بَيْنَهُمْ ۚ وَإِنَّهُمْ لَفِى شَكٍّ مِّنْهُ مُرِيبٍ ﴿٤٥﴾ مَّنْ عَمِلَ صَٰلِحًا
فَلِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَنْ أَسَآءَ فَعَلَيْهَا ۗ وَمَا رَبُّكَ بِظَلَّٰمٍ لِّلْعَبِيدِ ﴿٤٦﴾

(39) Yana kuma daga ayoyinsa cewa lalle za ka ga ƙasa a ƙeƙashe, to idan Mun saukar mata da ruwa sai ta girgiza ta kumbura (ta fitar da tsirrai). Lalle wanda Ya raya ta Shi ne Mai raya matattu. Lalle Shi Mai iko ne a kan komai

(40) Lalle waɗanda suke fanɗara game da ayoyinmu[1], ba za su ɓoyu gare Mu ba. Yanzu wanda za a jefa shi a cikin wuta, shi ya fi ko kuma wanda zai zo yana amintacce a ranar alƙiyama? Ku aikata abin da kuka ga dama, lalle Shi Mai ganin abin da kuke aikatawa ne

(41) Lalle waɗanda suka kafirce wa Alƙur'ani lokacin da ya zo musu (tabbas Allah zai saka musu). Lalle kuma shi littafi ne mabuwayi

(42) Ɓarna ba ta zuwa masa ta gabansa ko kuma ta bayansa; saukakke ne daga Mai hikima, Sha-yabo

(43) Ba abin da ake faɗa maka sai irin abin da aka faɗa wa manzanni a gabaninka[2]. Lalle Ubangijinka Mai gafara ne, kuma Mai uƙuba mai raɗaɗi ne

(44) Da Mun sanya shi Alƙur'ani Ba'ajame da tabbas za su ce: "Me ya hana a bayyana ayoyinsa? Yanzu (a ce Alƙur'ani) Ba'ajame (Annabi kuma) Balarabe?" Ka ce: "Shi ga waɗanda suka yi imani shiriya ne da waraka. Waɗanda kuwa ba sa yin imani akwai nauyi cikin kunnuwansu, shi kuma makanta ne a gare su." Waɗannan (sun yi kama da waɗanda) ake kira daga wuri mai nisa

(45) Haƙiƙa Mun bai wa Musa Littafin (Attaura), sai aka yi saɓani a cikinsa, kuma ba don Kalma ta gabata daga Ubangijinka ba, tabbas da an yi hukunci a tsakaninsu. Lalle kuma su, tabbas suna cikin shakka mai sa kokwanto a game da shi

(46) Wanda ya yi aiki nagari, to kansa ya yi wa, wanda kuma ya munana, to a kan kansa ya yi wa. Ubangijnka ba Mai zaluntar bayi ba ne

(1) Watau suke fanxare wa ayoyinsa, suna qaryata su, suna musunta su da jirkita ma'anoninsa ko canza lafuzansu.

(2) Watau na qaryata su da yi musu izgili.

إِلَيْهِ يُرَدُّ عِلْمُ ٱلسَّاعَةِ ۚ وَمَا تَخْرُجُ مِن ثَمَرَٰتٍ مِّنْ أَكْمَامِهَا
وَمَا تَحْمِلُ مِنْ أُنثَىٰ وَلَا تَضَعُ إِلَّا بِعِلْمِهِۦ ۚ وَيَوْمَ يُنَادِيهِمْ أَيْنَ
شُرَكَآءِى قَالُوٓا۟ ءَاذَنَّٰكَ مَا مِنَّا مِن شَهِيدٍ ﴿٤٧﴾ وَضَلَّ عَنْهُم
مَّا كَانُوا۟ يَدْعُونَ مِن قَبْلُ ۖ وَظَنُّوا۟ مَا لَهُم مِّن مَّحِيصٍ ﴿٤٨﴾
لَّا يَسْـَٔمُ ٱلْإِنسَٰنُ مِن دُعَآءِ ٱلْخَيْرِ وَإِن مَّسَّهُ ٱلشَّرُّ فَيَـُٔوسٌ
قَنُوطٌ ﴿٤٩﴾ وَلَئِنْ أَذَقْنَٰهُ رَحْمَةً مِّنَّا مِنۢ بَعْدِ ضَرَّآءَ مَسَّتْهُ
لَيَقُولَنَّ هَٰذَا لِى وَمَآ أَظُنُّ ٱلسَّاعَةَ قَآئِمَةً وَلَئِن رُّجِعْتُ إِلَىٰ
رَبِّىٓ إِنَّ لِى عِندَهُۥ لَلْحُسْنَىٰ ۚ فَلَنُنَبِّئَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِمَا عَمِلُوا۟
وَلَنُذِيقَنَّهُم مِّنْ عَذَابٍ غَلِيظٍ ﴿٥٠﴾ وَإِذَآ أَنْعَمْنَا عَلَى ٱلْإِنسَٰنِ
أَعْرَضَ وَنَـَٔا بِجَانِبِهِۦ ۖ وَإِذَا مَسَّهُ ٱلشَّرُّ فَذُو دُعَآءٍ عَرِيضٍ
﴿٥١﴾ قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِن كَانَ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ ثُمَّ كَفَرْتُم بِهِۦ
مَنْ أَضَلُّ مِمَّنْ هُوَ فِى شِقَاقٍۭ بَعِيدٍ ﴿٥٢﴾ سَنُرِيهِمْ ءَايَٰتِنَا
فِى ٱلْءَافَاقِ وَفِىٓ أَنفُسِهِمْ حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَهُمْ أَنَّهُ ٱلْحَقُّ ۗ
أَوَلَمْ يَكْفِ بِرَبِّكَ أَنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ شَهِيدٌ ﴿٥٣﴾ أَلَآ إِنَّهُمْ
فِى مِرْيَةٍ مِّن لِّقَآءِ رَبِّهِمْ ۗ أَلَآ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَىْءٍ مُّحِيطٌۢ ﴿٥٤﴾

(47) Gare shi ne ake mayar da sanin lokacin alkiyama. Kuma babu wasu ‘ya’yan itatuwa da suke fitowa daga kwansonsu, babu kuma wata mace da take ɗaukan ciki ko take haifewa sai da saninsa. Kuma a ranar da zai yi kiran su cewa: “Ina abokan tarayyar tawa?” Za su ce: “Mun sanar da Kai (a yau) babu wani mai yin shaida daga cikinmu[1].”

(48) Kuma abin da suka kasance suna bauta wa a da ya ɓace musu, suka kuma tabbatar ba su da wata matsera

(49) Mutum ba ya ƙosawa wajen roƙon alheri, idan kuwa wani sharri ya same shi, to sai ya zama mai tsananin ɗebe ƙauna

(50) Tabbas kuma idan Muka ɗanɗana masa wata rahama tamu bayan wata cuta da ta same shi, tabbas zai riƙa cewa: “Wannan nawa ne, kuma ba na tsammanin alkiyama za ta tashi, kuma tabbas idan ma da za a mayar da ni zuwa ga Ubangijina, lalle zan zama mai samun mafi kyan sakamako a wurinsa.” To tabbas za Mu saka wa waɗanda suka kafirta da abin da suka aikata, kuma tabbas za Mu ɗanɗana musu azaba mai gwaɓi

(51) Idan kuma Muka yi wa mutum ni’ima sai ya bijire ya ja jikinsa nesa (daga tuna Allah), kuma idan sharri ya same shi, sai ya zama mai faffaɗar addu’a

(52) Ka ce: “Ku ba ni labari, idan (Alƙur’ani) ya kasance daga wajen Allah, sannan kuka kafirce masa, to wane ne ya fi ɓata fiye da wanda yake cikin saɓani mai nisa?”

(53) Ba da daɗewa ba za Mu nuna musu ayoyinmu a cikin nahiyoyi da kuma a kan kawunansu har sai sun gane cewa lalle shi (Alƙur’ani) gaskiya ne. Yanzu bai ishe ka ba game da Ubangijinka cewa Shi lalle Mai shaida ne a kan komai?

(54) Ku saurara, lalle su suna cikin kokwanto ne game da haɗuwa da Ubangijnsu. Ku saurara, lalle Shi Mai kewaye komai ne da saninsa

(1) Watau babu wani da zai ba da shaidar cewa, Allah yana da abokan tarayya.

Sura Shura

سُورَةُ الشُّورَىٰ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حمٓ ﴿١﴾ عٓسٓقٓ ﴿٢﴾ كَذَٰلِكَ يُوحِيٓ إِلَيْكَ وَإِلَى الَّذِينَ مِن قَبْلِكَ
اللَّهُ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ ﴿٣﴾ لَهُۥ مَا فِي السَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ ۖ
وَهُوَ الْعَلِيُّ الْعَظِيمُ ﴿٤﴾ تَكَادُ السَّمَٰوَٰتُ يَتَفَطَّرْنَ مِن فَوْقِهِنَّ ۚ
وَالْمَلَٰٓئِكَةُ يُسَبِّحُونَ بِحَمْدِ رَبِّهِمْ وَيَسْتَغْفِرُونَ لِمَن فِي
الْأَرْضِ ۗ أَلَآ إِنَّ اللَّهَ هُوَ الْغَفُورُ الرَّحِيمُ ﴿٥﴾ وَالَّذِينَ اتَّخَذُوا۟
مِن دُونِهِۦٓ أَوْلِيَآءَ اللَّهُ حَفِيظٌ عَلَيْهِمْ وَمَآ أَنتَ عَلَيْهِم بِوَكِيلٍ
﴿٦﴾ وَكَذَٰلِكَ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ قُرْءَانًا عَرَبِيًّا لِّتُنذِرَ أُمَّ الْقُرَىٰ وَمَنْ
حَوْلَهَا وَتُنذِرَ يَوْمَ الْجَمْعِ لَا رَيْبَ فِيهِ ۚ فَرِيقٌ فِي الْجَنَّةِ وَفَرِيقٌ فِي
السَّعِيرِ ﴿٧﴾ وَلَوْ شَآءَ اللَّهُ لَجَعَلَهُمْ أُمَّةً وَٰحِدَةً وَلَٰكِن يُدْخِلُ مَن
يَشَآءُ فِي رَحْمَتِهِۦ ۚ وَالظَّٰلِمُونَ مَا لَهُم مِّن وَلِيٍّ وَلَا نَصِيرٍ ﴿٨﴾ أَمِ
اتَّخَذُوا۟ مِن دُونِهِۦٓ أَوْلِيَآءَ ۖ فَاللَّهُ هُوَ الْوَلِيُّ وَهُوَ يُحْىِ الْمَوْتَىٰ وَهُوَ
عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٩﴾ وَمَا اخْتَلَفْتُمْ فِيهِ مِن شَىْءٍ فَحُكْمُهُۥٓ
إِلَى اللَّهِ ۚ ذَٰلِكُمُ اللَّهُ رَبِّى عَلَيْهِ تَوَكَّلْتُ وَإِلَيْهِ أُنِيبُ ﴿١٠﴾

(1) HA MIM
(2) AIN SIN KAF [1] .
(3) Kamar haka ne Allah Mabuwayi, Mai hikima Yake yi maka wahayi da kuma waɗanda suka gabace ka
(4) Abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nasa ne; kuma Shi Maɗaukaki ne, Mai girma
(5) Sammai suna neman su tsattsage ta samansu (don girmansa). Mala'iku kuma suna yin tasbihi da yabon Ubangijinsu, suna kuma neman gafara ga waɗanda suke cikin ƙasa. Ku saurara, Lalle Allah Shi ne Mai gafara, Mai rahama
(6) Waɗanda kuwa suka riƙi wasu majiɓinta ba shi ba, Allah Mai kiyaye da su ne, kai kuma ba wakili ne ba a kansu
(7) Kuma kamar haka Muka yiwo maka wahayin Alƙur'ani Balarabe, don ka gargaɗi mutanen Makka da waɗanda suke kewaye da ita (watau duniya baki ɗaya), ka kuma yi gargaɗin ranar taruwa da babu kokwanto a game da ita. Wata ƙungiya tana cikin Aljanna, wata ƙungiya kuma tana cikin wutar Sa'ira
(8) Da kuma Allah Ya ga dama da Ya sanya su al'umma ɗaya (watau a kan addini ɗaya), sai dai kuma Yana shigar da wanda Ya ga dama cikin rahamarsa. Azzalumai kuma ba su da wani majiɓinci ko wani mataimaki
(9) Ko dai sun riƙi wasu majiɓinta ne ba Shi ba. To Allah Shi ne Majiɓinci, Shi ne kuma Yake raya matattu, Shi kuma Mai iko ne a kan komai
(10) Kuma duk wani abu da kuka yi saɓani a kansa, to sai ku mai da hukuncinsa ga Allah. Wannan Shi ne Allah Ubangijina, gare Shi kawai na dogara, kuma wurinsa kawai nake mayar da al'amarina

(1) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8.

فَاطِرُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ جَعَلَ لَكُم مِّنْ أَنفُسِكُمْ أَزْوَٰجًا
وَمِنَ ٱلْأَنْعَٰمِ أَزْوَٰجًا ۖ يَذْرَؤُكُمْ فِيهِ ۚ لَيْسَ كَمِثْلِهِۦ شَىْءٌ ۖ وَهُوَ
ٱلسَّمِيعُ ٱلْبَصِيرُ ﴿١١﴾ لَهُۥ مَقَالِيدُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ يَبْسُطُ
ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقْدِرُ ۚ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿١٢﴾ ۞ شَرَعَ
لَكُم مِّنَ ٱلدِّينِ مَا وَصَّىٰ بِهِۦ نُوحًا وَٱلَّذِىٓ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ وَمَا
وَصَّيْنَا بِهِۦٓ إِبْرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَىٰٓ ۖ أَنْ أَقِيمُوا۟ ٱلدِّينَ
وَلَا تَتَفَرَّقُوا۟ فِيهِ ۚ كَبُرَ عَلَى ٱلْمُشْرِكِينَ مَا تَدْعُوهُمْ إِلَيْهِ ۚ ٱللَّهُ
يَجْتَبِىٓ إِلَيْهِ مَن يَشَآءُ وَيَهْدِىٓ إِلَيْهِ مَن يُنِيبُ ﴿١٣﴾ وَمَا تَفَرَّقُوٓا۟
إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلْعِلْمُ بَغْيًۢا بَيْنَهُمْ ۚ وَلَوْلَا كَلِمَةٌ سَبَقَتْ
مِن رَّبِّكَ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى لَّقُضِىَ بَيْنَهُمْ ۚ وَإِنَّ ٱلَّذِينَ أُورِثُوا۟
ٱلْكِتَٰبَ مِنۢ بَعْدِهِمْ لَفِى شَكٍّ مِّنْهُ مُرِيبٍ ﴿١٤﴾ فَلِذَٰلِكَ
فَٱدْعُ ۖ وَٱسْتَقِمْ كَمَآ أُمِرْتَ ۖ وَلَا تَتَّبِعْ أَهْوَآءَهُمْ ۖ وَقُلْ
ءَامَنتُ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ مِن كِتَٰبٍ ۖ وَأُمِرْتُ لِأَعْدِلَ بَيْنَكُمُ ۖ
ٱللَّهُ رَبُّنَا وَرَبُّكُمْ ۖ لَنَآ أَعْمَٰلُنَا وَلَكُمْ أَعْمَٰلُكُمْ ۖ لَا حُجَّةَ
بَيْنَنَا وَبَيْنَكُمُ ۖ ٱللَّهُ يَجْمَعُ بَيْنَنَا ۖ وَإِلَيْهِ ٱلْمَصِيرُ ﴿١٥﴾

(11) (Shi ne) Mahaliccin sammai da ƙasa. Ya halitta muku mataye daga jinsinku, daga dabbobi ma (Ya halicce su) maza da mata; Yana yaɗa ku ta hanyarsa (haɗin jinsin biyu). Babu wani abu da ya yi kama da Shi(1); kuma Shi Mai ji ne, Mai gani

(12) Mabuɗan taskokin sammai da ƙasa nasa ne; Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, yana kuma ƙuntatawa. Lalle shi Masanin komai ne

(13) En materia de religión, les ha sido Ya shar'anta muku (irin) abin da Ya yi wa Nuhu wahayi da shi na addini, da kuma wanda Muka yiwo maka wahayinsa, da kuma abin da Muka yi wa Ibrahimu da Musa da Isa wasiyya da shi cewa: "Ku tsayar da addini, kuma kada ku rarraba a cikinsa." Abin da kake kiran kafirai zuwa gare shi ya yi musu nauyi. Allah Yana zaɓar wanda Ya ga dama zuwa gare shi (addini) Yana kuma shiryar da wanda Ya mayar da al'amarinsa zuwa gare Shi

(14) Y (los seguidores de las otras religiones) no se dibidieron (y separaron) hasta Ba su kuma rarrabu ba sai bayan ilimi ya zo musu don zalunci da ke tsakaninsu. Ba don kalmar da ta riga ta gabata daga Ubangijinka ba (ta jinkirta musu) zuwa ga wani lokaci ƙayyadajje, da lalle an yi hukunci tsakaninsu. Kuma lalle waɗanda aka gadar wa da littafi a bayansu lallai suna cikin shakka mai sa kokwanto game da shi (Annabi Muhammadu)

(15) Saboda wannan sai ka yi kira (zuwa ga addinin Allah), kuma ka tsaya kyam kamar yadda aka umarce ka, kada ka bi son ransu; ka kuma ce: "Na yi imani da abin da Allah Ya saukar na littattafai; an kuma umarce ni da yin adalci a tsakaninku; Allah ne Ubangijinmu kuma Ubangijinku; (sakamakon) ayyukanmu namu ne, ku ma (sakamakon) ayyukanku naku ne; babu wata jayayya a tsakaninmu da ku; Allah zai tara mu; kuma zuwa gare Shi ne kaɗai makoma

(1) Watau ba ya da mai kama da shi a Zatinsa da siffofinsa da sunayensa da ayyukansa.

وَٱلَّذِينَ يُحَآجُّونَ فِى ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مَا ٱسۡتُجِيبَ لَهُۥ حُجَّتُهُمۡ
دَاحِضَةٌ عِندَ رَبِّهِمۡ وَعَلَيۡهِمۡ غَضَبٞ وَلَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدٌ
١٦ ٱللَّهُ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ وَٱلۡمِيزَانَۗ وَمَا يُدۡرِيكَ
لَعَلَّ ٱلسَّاعَةَ قَرِيبٞ ١٧ يَسۡتَعۡجِلُ بِهَا ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ
بِهَاۖ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مُشۡفِقُونَ مِنۡهَا وَيَعۡلَمُونَ أَنَّهَا ٱلۡحَقُّۗ
أَلَآ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُمَارُونَ فِى ٱلسَّاعَةِ لَفِى ضَلَٰلِۭ بَعِيدٍ ١٨
ٱللَّهُ لَطِيفُۢ بِعِبَادِهِۦ يَرۡزُقُ مَن يَشَآءُۖ وَهُوَ ٱلۡقَوِىُّ ٱلۡعَزِيزُ
١٩ مَن كَانَ يُرِيدُ حَرۡثَ ٱلۡأٓخِرَةِ نَزِدۡ لَهُۥ فِى حَرۡثِهِۦۖ وَمَن
كَانَ يُرِيدُ حَرۡثَ ٱلدُّنۡيَا نُؤۡتِهِۦ مِنۡهَا وَمَا لَهُۥ فِى ٱلۡأٓخِرَةِ
مِن نَّصِيبٍ ٢٠ أَمۡ لَهُمۡ شُرَكَٰٓؤُاْ شَرَعُواْ لَهُم مِّنَ ٱلدِّينِ
مَا لَمۡ يَأۡذَنۢ بِهِ ٱللَّهُۚ وَلَوۡلَا كَلِمَةُ ٱلۡفَصۡلِ لَقُضِىَ بَيۡنَهُمۡۗ
وَإِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٢١ تَرَى ٱلظَّٰلِمِينَ
مُشۡفِقِينَ مِمَّا كَسَبُواْ وَهُوَ وَاقِعُۢ بِهِمۡۗ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فِى رَوۡضَاتِ ٱلۡجَنَّاتِۖ لَهُم
مَّا يَشَآءُونَ عِندَ رَبِّهِمۡۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَضۡلُ ٱلۡكَبِيرُ ٢٢

(16) Waɗanda kuma suke jayayya game da Allah bayan an amsa masa (kiransa), to hujjarsu ɓatacciya ce a wurin Ubangijinsu, kuma fushi ya hau kansu, kuma suna da azaba mai tsanani

(17) Allah ne Ya saukar da Littafi da gaskiya da kuma adalci. Me yake sanar da kai cewa ko alƙiyama kusa take

(18) Waɗanda ba sa yin imani da ita suna gaggauto da ita; waɗanda kuwa suka yi imani a tsorace suke da ita, kuma suna sane da cewa ita gaskiya ce. Ku saurara, lalle waɗanda suke jayayya game da tashin alƙiyama tabbas suna cikin ɓata mai nisa

(19) Allah Mai tausasa wa bayinsa ne, Yana arzuta wanda ya ga dama; kuma Shi Kaƙƙarfa ne, Mabuwayi

(20) Wanda ya kasance yana nufin ladan lahira to za Mu ƙara masa a kan ladansa; wanda kuwa ya kasance yana nufin ladan duniya to za Mu ba shi (wani abu) daga gare ta, kuma ba shi da wani rabo a lahira

(21) Ko dai suna da wasu abokan tarayya ne da suka shar'anta musu wani abu na addini wanda Allah bai yi izinin yin sa ba? Ba don kalmar yin hukunci (a lahira) ta tabbata ba, da lalle an yi hukunci a tsakaninsu (tun a duniya). Lalle kuma azzalumai suna da azaba mai raɗaɗi

(22) (Za ka ga azzalumai suna tsoron sakamakon abin da suka aikata, alhali kuwa ga shi zai faɗa musu. Waɗanda kuwa suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, to suna cikin dausayoyin gidajen Aljanna; suna samun duk abin da suka ga dama a wurin Ubangijinsu. Wannan ita ce falala mai girma

ذَٰلِكَ ٱلَّذِى يُبَشِّرُ ٱللَّهُ عِبَادَهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ ۗ
قُل لَّآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ أَجْرًا إِلَّا ٱلْمَوَدَّةَ فِى ٱلْقُرْبَىٰ ۗ وَمَن يَقْتَرِفْ
حَسَنَةً نَّزِدْ لَهُۥ فِيهَا حُسْنًا ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ شَكُورٌ ﴿٢٣﴾ أَمْ يَقُولُونَ
ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا ۖ فَإِن يَشَإِ ٱللَّهُ يَخْتِمْ عَلَىٰ قَلْبِكَ ۗ وَيَمْحُ ٱللَّهُ
ٱلْبَٰطِلَ وَيُحِقُّ ٱلْحَقَّ بِكَلِمَٰتِهِۦٓ ۚ إِنَّهُۥ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿٢٤﴾
وَهُوَ ٱلَّذِى يَقْبَلُ ٱلتَّوْبَةَ عَنْ عِبَادِهِۦ وَيَعْفُوا۟ عَنِ ٱلسَّيِّـَٔاتِ
وَيَعْلَمُ مَا تَفْعَلُونَ ﴿٢٥﴾ وَيَسْتَجِيبُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟
ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَيَزِيدُهُم مِّن فَضْلِهِۦ ۚ وَٱلْكَٰفِرُونَ لَهُمْ عَذَابٌ
شَدِيدٌ ﴿٢٦﴾ ۞ وَلَوْ بَسَطَ ٱللَّهُ ٱلرِّزْقَ لِعِبَادِهِۦ لَبَغَوْا۟ فِى ٱلْأَرْضِ
وَلَٰكِن يُنَزِّلُ بِقَدَرٍ مَّا يَشَآءُ ۚ إِنَّهُۥ بِعِبَادِهِۦ خَبِيرٌۢ بَصِيرٌ ﴿٢٧﴾ وَهُوَ
ٱلَّذِى يُنَزِّلُ ٱلْغَيْثَ مِنۢ بَعْدِ مَا قَنَطُوا۟ وَيَنشُرُ رَحْمَتَهُۥ ۚ وَهُوَ ٱلْوَلِىُّ ٱلْحَمِيدُ
﴿٢٨﴾ وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦ خَلْقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَثَّ فِيهِمَا مِن دَآبَّةٍ ۚ
وَهُوَ عَلَىٰ جَمْعِهِمْ إِذَا يَشَآءُ قَدِيرٌ ﴿٢٩﴾ وَمَآ أَصَٰبَكُم مِّن مُّصِيبَةٍ فَبِمَا
كَسَبَتْ أَيْدِيكُمْ وَيَعْفُوا۟ عَن كَثِيرٍ ﴿٣٠﴾ وَمَآ أَنتُم بِمُعْجِزِينَ
فِى ٱلْأَرْضِ ۖ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن وَلِىٍّ وَلَا نَصِيرٍ ﴿٣١﴾

(23) Wannan fa shi ne abin da Allah Yake yin albishir da shi ga bayinsa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari. Ka ce: “Ba na tambayar ku wani lada a kansa (isar da saƙon), sai dai kawai soyayya ta zumunta”. Duk wanda ya aikata wani aiki kyakkyawa za Mu ƙara masa kyakkyawan sakamako a kansa. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai godiya

(24) A’a, suna dai cewa ya ƙaga wa Allah ƙarya ne; to da Allah Ya ga dama da sai Ya rufe zuciyarka(1). Allah kuma Yana shafe ƙarya Yana kuma tabbatar da gaskiya da kalmominsa. Lalle Shi Masanin abubuwan da suke cikin zukata ne

(25) Shi ne kuma wanda Yake karɓar tuba daga bayinsa, Yake kuma yin afuwa game da munanan (ayyuka), Yana kuma sane da abin da kuke aikatawa

(26) Kuma Yana amsa wa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, Yana kuma ƙara musu daga falalarsa. Kafirai kuwa suna da azaba mai tsanani

(27) Da kuma Allah Ya shimfiɗa wa bayinsa arziki to da sun yi tsaurin kai a bayan ƙasa, sai dai kuma Yana saukarwa ne daidai gwargwado yadda Ya ga dama. Lalle Shi Masani ne game da bayinsa, Mai ganin (ayyukansu)

(28) Shi ne kuma Yake saukar da ruwan sama bayan sun ɗebe ƙauna, Ya kuma yaɗa rahamarsa. Kuma Shi ne Majiɓincin al’amura, Sha-yabo

(29) Yana kuma daga cikin ayoyinsa halittar sammai da ƙasa da kuma dabbobin da Ya yaɗa a cikinsu. Kuma shi Mai iko ne a kan Ya tara su idan Ya ga dama

(30) Abin da kuma ya same ku na wata masifa, to saboda abin da hannayenku ne suka tsuwurwurta, Yana kuma yin afuwa ga wasu (laifuka) masu yawa

(31) Kuma ku ba za ku gagara ba a bayan ƙasa; kuma ba ku da wani majiɓinci ko mataimaki in ba Allah ba

(1) Watau da a ce zuciyarsa ta riya masa ya qirqiri Alqur’ani da kansa ya jingina wa Allah, to da Allah ya toshe masa zuciyarsa yadda ba zai qara fahimtar komai ba.

وَمِنْ ءَايَٰتِهِ ٱلْجَوَارِ فِى ٱلْبَحْرِ كَٱلْأَعْلَٰمِ ﴿٣٢﴾ إِن يَشَأْ يُسْكِنِ ٱلرِّيحَ
فَيَظْلَلْنَ رَوَاكِدَ عَلَىٰ ظَهْرِهِۦٓ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّكُلِّ صَبَّارٍ شَكُورٍ
﴿٣٣﴾ أَوْ يُوبِقْهُنَّ بِمَا كَسَبُوا۟ وَيَعْفُ عَن كَثِيرٍ ﴿٣٤﴾ وَيَعْلَمَ ٱلَّذِينَ
يُجَٰدِلُونَ فِىٓ ءَايَٰتِنَا مَا لَهُم مِّن مَّحِيصٍ ﴿٣٥﴾ فَمَآ أُوتِيتُم مِّن شَىْءٍ فَمَتَٰعُ
ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ وَمَا عِندَ ٱللَّهِ خَيْرٌ وَأَبْقَىٰ لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَلَىٰ رَبِّهِمْ
يَتَوَكَّلُونَ ﴿٣٦﴾ وَٱلَّذِينَ يَجْتَنِبُونَ كَبَٰٓئِرَ ٱلْإِثْمِ وَٱلْفَوَٰحِشَ وَإِذَا مَا
غَضِبُوا۟ هُمْ يَغْفِرُونَ ﴿٣٧﴾ وَٱلَّذِينَ ٱسْتَجَابُوا۟ لِرَبِّهِمْ وَأَقَامُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ
وَأَمْرُهُمْ شُورَىٰ بَيْنَهُمْ وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ يُنفِقُونَ ﴿٣٨﴾ وَٱلَّذِينَ إِذَآ أَصَابَهُمُ
ٱلْبَغْىُ هُمْ يَنتَصِرُونَ ﴿٣٩﴾ وَجَزَٰٓؤُا۟ سَيِّئَةٍ سَيِّئَةٌ مِّثْلُهَا ۖ فَمَنْ عَفَا
وَأَصْلَحَ فَأَجْرُهُۥ عَلَى ٱللَّهِ ۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٤٠﴾ وَلَمَنِ ٱنتَصَرَ
بَعْدَ ظُلْمِهِۦ فَأُو۟لَٰٓئِكَ مَا عَلَيْهِم مِّن سَبِيلٍ ﴿٤١﴾ إِنَّمَا ٱلسَّبِيلُ عَلَى
ٱلَّذِينَ يَظْلِمُونَ ٱلنَّاسَ وَيَبْغُونَ فِى ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ
لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٤٢﴾ وَلَمَن صَبَرَ وَغَفَرَ إِنَّ ذَٰلِكَ لَمِنْ عَزْمِ
ٱلْأُمُورِ ﴿٤٣﴾ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن وَلِىٍّ مِّنۢ بَعْدِهِۦ ۗ وَتَرَى
ٱلظَّٰلِمِينَ لَمَّا رَأَوُا۟ ٱلْعَذَابَ يَقُولُونَ هَلْ إِلَىٰ مَرَدٍّ مِّن سَبِيلٍ ﴿٤٤﴾

(32) Daga cikin ayoyinsa kuma akwai jiragen ruwa masu gudu a cikin kogi kamar duwatsu
(33) Idan da Ya ga dama da sai Ya kwantar da iska sai (jiragen) su zama a tsaye cak a kan (kogin). Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga duk wani mai yawan haƙuri, mai yawan godiya
(34) Ko kuma Ya nutsar da su saboda (munanan ayyukan) da suka aikata. Ko kuma ya yi afuwa ga wasu (laifuka) masu yawa
(35) Kuma waɗanda suke jayayya game da ayoyinmu sun san da cewa ba su da wata matsera

(36) Sannan duk wani abu da aka ba ku to jin daɗin rayuwar duniya ne; kuma abin da yake wurin Allah shi ya fi alheri ya kuma fi wanzuwa ga waɗanda suka yi imani suke kuma dogara ga Ubangijinsu
(37) Waɗanda kuma suke nesantar manyan zunubai da munanansu, idan kuma sun yi fushi sukan yafe
(38) (Su ne) kuma waɗanda suka amsa kiran Ubangijinsu suka kuma tsai da salla, al'amarinsu kuwa (suna) shawara ne a tsakaninsu, suna kuma ciyarwa daga abin da Muka arzuta su
(39) (Su ne) kuma waɗanda idan wani zalunci ya shafe su sukan rama[1]
(40) Kuma sakamakon mummunan (abu) shi ne mayar da mummuna kamarsa; to wanda ya yi afuwa ya kuma kyautata, to ladansa yana wurin Allah. Lalle Shi ba Ya son azzalumai
(41) Tabbas kuma duk wanda ya rama bayan an zalunce shi, to waɗannan ba wani laifi a kansu
(42) Laifi kam yana kan waɗanda suke zaluntar mutane ne suke kuma yin ta'adda a bayan ƙasa ba da wata hujja ba. Waɗannan suna da azaba mai raɗaɗi
(43)Tabbas kuma wanda ya yi haƙuri ya yafe, to tabbas wannan yana daga muhimman al'amura[2]
(44) Wanda kuma Allah Ya ɓatar, to ba shi da wani majiɓinci bayanSa. Kuma za ka ga azzalumai lokacin da suka ga azabar suna cewa: "Ina ma da akwai wata damar komawa (duniya)?"

(1) Yayin da azzalumin ya kasance ba wanda ya cancanci afuwa ba ne, kuma babu maslaha cikin yi masa afuwar.

(2) Watau haqurinsa zai zame masa alheri, har ma da al'ummarsa gaba xaya.

وَتَرَىٰهُمْ يُعْرَضُونَ عَلَيْهَا خَٰشِعِينَ مِنَ ٱلذُّلِّ يَنظُرُونَ
مِن طَرْفٍ خَفِيٍّ ۗ وَقَالَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِنَّ ٱلْخَٰسِرِينَ ٱلَّذِينَ
خَسِرُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ وَأَهْلِيهِمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۗ أَلَآ إِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ
فِى عَذَابٍ مُّقِيمٍ ﴿٤٥﴾ وَمَا كَانَ لَهُم مِّنْ أَوْلِيَآءَ يَنصُرُونَهُم
مِّن دُونِ ٱللَّهِ ۗ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن سَبِيلٍ ﴿٤٦﴾ ٱسْتَجِيبُوا۟
لِرَبِّكُم مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِىَ يَوْمٌ لَّا مَرَدَّ لَهُۥ مِنَ ٱللَّهِ ۚ مَا لَكُم
مِّن مَّلْجَإٍ يَوْمَئِذٍ وَمَا لَكُم مِّن نَّكِيرٍ ﴿٤٧﴾ فَإِنْ أَعْرَضُوا۟
فَمَآ أَرْسَلْنَٰكَ عَلَيْهِمْ حَفِيظًا ۖ إِنْ عَلَيْكَ إِلَّا ٱلْبَلَٰغُ ۗ وَإِنَّآ إِذَآ
أَذَقْنَا ٱلْإِنسَٰنَ مِنَّا رَحْمَةً فَرِحَ بِهَا ۖ وَإِن تُصِبْهُمْ سَيِّئَةٌۢ
بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ فَإِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ كَفُورٌ ﴿٤٨﴾ لِّلَّهِ مُلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ ۚ يَهَبُ لِمَن يَشَآءُ إِنَٰثًا
وَيَهَبُ لِمَن يَشَآءُ ٱلذُّكُورَ ﴿٤٩﴾ أَوْ يُزَوِّجُهُمْ ذُكْرَانًا وَإِنَٰثًا ۖ
وَيَجْعَلُ مَن يَشَآءُ عَقِيمًا ۚ إِنَّهُۥ عَلِيمٌ قَدِيرٌ ﴿٥٠﴾ ۞ وَمَا كَانَ
لِبَشَرٍ أَن يُكَلِّمَهُ ٱللَّهُ إِلَّا وَحْيًا أَوْ مِن وَرَآئِ حِجَابٍ أَوْ يُرْسِلَ
رَسُولًا فَيُوحِىَ بِإِذْنِهِۦ مَا يَشَآءُ ۚ إِنَّهُۥ عَلِىٌّ حَكِيمٌ ﴿٥١﴾

(45) Kuma za ka gan su ana bijiro su a kanta (wutar) suna masu ƙanƙan da kai na wulaƙanci, suna kallo a sace. Waɗanda kuma suka yi imani suka ce: “Lalle asararru su ne waɗanda suka yi asarar rayuwarsu da ta iyalinsu a ranar alƙiyama.” Ku saurara, lalle azzalumai suna cikin azaba dawwamammiya

(46) Kuma ba su da wasu majiɓinta da za su taimake su in ban da Allah. Duk wanda Allah Ya ɓatar, to ba shi da wata hanya daban (ta shiriya)

(47) Ku amsa kiran Ubangijinku tun kafin ranar da ba ta da wata makauta[1] ta zo daga Allah. Ba ku da wata mafaka a wannan ranar, kuma ba ku da damar yin musu[2]

(48) To idan sun bijire, to ba Mu aika ka don ka zama mai gadin su ba; ba abin da yake kanka sai isar da saƙo. Lalle kuma Mu idan Muka ɗanɗana wa mutum wata rahama daga gare Mu sai ya riƙa tutiya da ita. Idan kuma wani mummunan abu ya same su saboda abin da hannayensu suka aikata, to lalle shi mutum butulu ne

(49) Mulkin sammai da ƙasa na Allah ne. Yana halittar abin da Ya ga dama. Yana ba da `ya`ya mata ga wanda Ya ga dama, Yana kuma ba da `ya`ya maza ga wanda Ya ga dama

(50) Ko kuma ya haɗa musu maza da mata; Yakan kuma mayar da wanda ya ga dama bakarare. Lalle Shi Masani ne, Mai iko

(51) Kuma zai yiwu ga wani mutum a ce Allah Ya yi magana da shi ba (baki da baki), sai dai wahayi ko kuma ta bayan wani shamaki, ko kuwa Ya aiko wani manzo (mala’ika) sai ya yi masa wahayin abin da ya ga dama da yardarsa. Lalle Shi Maɗaukaki ne, Mai hikima

(1) Watau babu wanda ya isa ya hana zuwanta.

(2) Watau ba su da damar musunta zunuban da suka aikata a duniya.

وَكَذَٰلِكَ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ رُوحًا مِّنْ أَمْرِنَا ۚ مَا كُنتَ تَدْرِى مَا ٱلْكِتَٰبُ
وَلَا ٱلْإِيمَٰنُ وَلَٰكِن جَعَلْنَٰهُ نُورًا نَّهْدِى بِهِۦ مَن نَّشَآءُ مِنْ عِبَادِنَا ۚ
وَإِنَّكَ لَتَهْدِىٓ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٥٢﴾ صِرَٰطِ ٱللَّهِ ٱلَّذِى لَهُۥ
مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۗ أَلَآ إِلَى ٱللَّهِ تَصِيرُ ٱلْأُمُورُ ﴿٥٣﴾

سُورَةُ الزُّخْرُفِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

حمٓ ﴿١﴾ وَٱلْكِتَٰبِ ٱلْمُبِينِ ﴿٢﴾ إِنَّا جَعَلْنَٰهُ قُرْءَٰنًا عَرَبِيًّا
لَّعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿٣﴾ وَإِنَّهُۥ فِىٓ أُمِّ ٱلْكِتَٰبِ لَدَيْنَا
لَعَلِىٌّ حَكِيمٌ ﴿٤﴾ أَفَنَضْرِبُ عَنكُمُ ٱلذِّكْرَ صَفْحًا
أَن كُنتُمْ قَوْمًا مُّسْرِفِينَ ﴿٥﴾ وَكَمْ أَرْسَلْنَا مِن نَّبِىٍّ فِى
ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٦﴾ وَمَا يَأْتِيهِم مِّن نَّبِىٍّ إِلَّا كَانُوا۟ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ
﴿٧﴾ فَأَهْلَكْنَآ أَشَدَّ مِنْهُم بَطْشًا وَمَضَىٰ مَثَلُ ٱلْأَوَّلِينَ
﴿٨﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ
خَلَقَهُنَّ ٱلْعَزِيزُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٩﴾ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَرْضَ
مَهْدًا وَجَعَلَ لَكُمْ فِيهَا سُبُلًا لَّعَلَّكُمْ تَهْتَدُونَ ﴿١٠﴾

(52) Kuma kamar haka ne Muka yiwo maka wahayin Ruhi (watau Alƙur'ani) daga umarninmu. Ba ka zamanto ka san mene ne littafi ko kuma imani ba, sai dai kuma Mun sanya shi (Alƙur'ani) haske ne da Muke shiryar da wanda Muka ga dama daga bayinmu da shi. Lalle kuma kai tabbas kana shiryarwa zuwa ga tafarki madaidaici
(53) (Watau) tafarkin Allah wanda Yake da mulkin abin da yake cikin sammai da abin da yake ƙasa. Ku saurara, zuwa ga Allah ne kawai al'amura suke komawa

Sura Zukhruf

(1) HA MIM[1] .
(2)Na rantse da Littafi mabayyani (Alƙur'ani)
(3)Lalle Mu Mun sanya shi ya zamo abin karantawa cikin harshen Larabci domin ku hankalta
(4) Lalle kuma shi (Alƙur'ani) a cikin Littafi Lauhul-Mahafuzu a wurinmu tabbas maɗaukaki ne, mai hikima
(5) Yanzu Ma fasa saukar muku da Alƙur'ani Mu watsar da ku, don kun kasance mutane masu yawan ɓarna?
(6) Annabi nawa Muka aika wa mutanen farko
(7) Ba kuma wani annabi da yakan zo musu sai sun kasance suna yi masa izgili
(8) Sai Muka hallakar da waɗanda suka fi su tsananin ƙarfi[2], kuma bayanin yadda aka hallakar da mutanen farko ya riga ya shuɗe
(9) Lalle kuma idan ka tambaye su wane ne ya halicci sammai da ƙasa, to tabbas za su ce: "(Allah) ne Mabuwayi, Masani Ya halicce su."
(10) Wanda Ya sanya muku ƙasa ta zama shimfiɗa, Ya kuma sanya muku hanyoyi a cikinta don ku gane (inda za ku dosa)

(1) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Watau kamar qabilun Adawa da Samudawa da mutanen Annabi Luxu ( ).

وَٱلَّذِى نَزَّلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءًۢ بِقَدَرٍ فَأَنشَرْنَا بِهِۦ بَلْدَةً مَّيْتًا ۚ
كَذَٰلِكَ تُخْرَجُونَ ﴿١١﴾ وَٱلَّذِى خَلَقَ ٱلْأَزْوَٰجَ كُلَّهَا وَجَعَلَ
لَكُم مِّنَ ٱلْفُلْكِ وَٱلْأَنْعَٰمِ مَا تَرْكَبُونَ ﴿١٢﴾ لِتَسْتَوُۥا۟ عَلَىٰ ظُهُورِهِۦ
ثُمَّ تَذْكُرُوا۟ نِعْمَةَ رَبِّكُمْ إِذَا ٱسْتَوَيْتُمْ عَلَيْهِ وَتَقُولُوا۟ سُبْحَٰنَ
ٱلَّذِى سَخَّرَ لَنَا هَٰذَا وَمَا كُنَّا لَهُۥ مُقْرِنِينَ ﴿١٣﴾ وَإِنَّآ إِلَىٰ رَبِّنَا
لَمُنقَلِبُونَ ﴿١٤﴾ وَجَعَلُوا۟ لَهُۥ مِنْ عِبَادِهِۦ جُزْءًا ۚ إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ
لَكَفُورٌ مُّبِينٌ ﴿١٥﴾ أَمِ ٱتَّخَذَ مِمَّا يَخْلُقُ بَنَٰتٍ وَأَصْفَىٰكُم
بِٱلْبَنِينَ ﴿١٦﴾ وَإِذَا بُشِّرَ أَحَدُهُم بِمَا ضَرَبَ لِلرَّحْمَٰنِ مَثَلًا
ظَلَّ وَجْهُهُۥ مُسْوَدًّا وَهُوَ كَظِيمٌ ﴿١٧﴾ أَوَمَن يُنَشَّؤُا۟ فِى
ٱلْحِلْيَةِ وَهُوَ فِى ٱلْخِصَامِ غَيْرُ مُبِينٍ ﴿١٨﴾ وَجَعَلُوا۟ ٱلْمَلَٰٓئِكَةَ
ٱلَّذِينَ هُمْ عِبَٰدُ ٱلرَّحْمَٰنِ إِنَٰثًا ۚ أَشَهِدُوا۟ خَلْقَهُمْ ۚ سَتُكْتَبُ
شَهَٰدَتُهُمْ وَيُسْـَٔلُونَ ﴿١٩﴾ وَقَالُوا۟ لَوْ شَآءَ ٱلرَّحْمَٰنُ مَا عَبَدْنَٰهُمْ ۗ
مَّا لَهُم بِذَٰلِكَ مِنْ عِلْمٍ ۖ إِنْ هُمْ إِلَّا يَخْرُصُونَ ﴿٢٠﴾ أَمْ ءَاتَيْنَٰهُمْ
كِتَٰبًا مِّن قَبْلِهِۦ فَهُم بِهِۦ مُسْتَمْسِكُونَ ﴿٢١﴾ بَلْ قَالُوٓا۟ إِنَّا
وَجَدْنَآ ءَابَآءَنَا عَلَىٰٓ أُمَّةٍ وَإِنَّا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم مُّهْتَدُونَ ﴿٢٢﴾

(11) Wanda kuma Ya saukar da ruwa daidai gwargwado daga sama sannan Muka raya mataccen gari da shi. Kamar haka ne za a fito da ku (daga ƙabarurruka)

(12) Kuma wanda Ya halicci dukkan dangogin abubuwa bibbiyu, Ya kuma sanya muku daga jiragen ruwa da kuma dabbobin ni'ima, abubuwan da kuke hawa

(13) Don ku daidaita a kan bayansu, sannan ku tuna ni'imar Ubangijinku lokacin da kuka daidaita a kansu kuma ku ce: "Tsarki ya tabbata ga wanda Ya hore mana wannan, ba mu zamanto masu ikon sarrafa shi ba

(14) "Kuma lalle zuwa ga Ubangijinmu tabbas za mu koma."

(15) Kuma suka mai da wasu daga cikin bayinsa wani ɓangare nasa (wato `ya`yansa). Lalle mutum mai yawan butulci ne mai bayyana (butulcinsa)

(16) Yanzu Ya ɗauki `ya`ya mata daga abubuwan da Yake halitta, ku kuma Ya zaɓa muku `ya`ya maza?

(17) Idan kuma aka yi wa ɗayansu albishir da abin da ya buga misali cewa na (Allah) Arrahmanu ne, sai fuskarsa ta yini a murtuke yana cike da baƙin ciki

(18) Yanzu (sa danganta wa Allah) wanda da ake renon sa cikin kwalliya, alhali kuma idan an zo wajen husuma ba zai iya bayyana kansa (wajan ba da hujja) ba?

(19) Suka kuma mai da mala'iku waɗanda suke bayin (Allah) Arrahmanu ne `ya`ya mata. Shin sun halarci sanda aka halicce su ne? To za a rubuta shaidarsu, za kuma a tambaye su (a lahira)

(20) Suka kuma ce: "Da (Allah) Arrahmanu Ya ga dama, da ba mu bauta musu ba (wato mala'ikun)." Ba su da wani takamaiman ilimi a kan hakan; ba abin da suke yi sai shaci-faɗi

(21) Ko kuma Mun ba su wani littafi ne gabaninsa (Alƙur'ani), saboda haka suke riƙe da shi ƙam-ƙam?

(22) A'a, cewa dai suka yi: "Lalle mu mun sami iyayenmu a kan wani addini ne, mu kuma lalle sawunsu muke bi."

وَكَذَٰلِكَ مَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ فِي قَرۡيَةٖ مِّن نَّذِيرٍ إِلَّا قَالَ مُتۡرَفُوهَآ
إِنَّا وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا عَلَىٰٓ أُمَّةٖ وَإِنَّا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم مُّقۡتَدُونَ ٢٣
* قَٰلَ أَوَلَوۡ جِئۡتُكُم بِأَهۡدَىٰ مِمَّا وَجَدتُّمۡ عَلَيۡهِ ءَابَآءَكُمۡۖ
قَالُوٓاْ إِنَّا بِمَآ أُرۡسِلۡتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ ٢٤ فَٱنتَقَمۡنَا مِنۡهُمۡۖ فَٱنظُرۡ
كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ ٢٥ وَإِذۡ قَالَ إِبۡرَٰهِيمُ لِأَبِيهِ وَقَوۡمِهِۦٓ
إِنَّنِي بَرَآءٞ مِّمَّا تَعۡبُدُونَ ٢٦ إِلَّا ٱلَّذِي فَطَرَنِي فَإِنَّهُۥ سَيَهۡدِينِ
٢٧ وَجَعَلَهَا كَلِمَةَۢ بَاقِيَةٗ فِي عَقِبِهِۦ لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ٢٨ بَلۡ
مَتَّعۡتُ هَٰٓؤُلَآءِ وَءَابَآءَهُمۡ حَتَّىٰ جَآءَهُمُ ٱلۡحَقُّ وَرَسُولٞ مُّبِينٞ ٢٩
وَلَمَّا جَآءَهُمُ ٱلۡحَقُّ قَالُواْ هَٰذَا سِحۡرٞ وَإِنَّا بِهِۦ كَٰفِرُونَ ٣٠ وَقَالُواْ
لَوۡلَا نُزِّلَ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانُ عَلَىٰ رَجُلٖ مِّنَ ٱلۡقَرۡيَتَيۡنِ عَظِيمٍ ٣١ أَهُمۡ
يَقۡسِمُونَ رَحۡمَتَ رَبِّكَۚ نَحۡنُ قَسَمۡنَا بَيۡنَهُم مَّعِيشَتَهُمۡ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ
ٱلدُّنۡيَاۚ وَرَفَعۡنَا بَعۡضَهُمۡ فَوۡقَ بَعۡضٖ دَرَجَٰتٖ لِّيَتَّخِذَ بَعۡضُهُم
بَعۡضٗا سُخۡرِيّٗاۗ وَرَحۡمَتُ رَبِّكَ خَيۡرٞ مِّمَّا يَجۡمَعُونَ ٣٢ وَلَوۡلَآ
أَن يَكُونَ ٱلنَّاسُ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ لَّجَعَلۡنَا لِمَن يَكۡفُرُ بِٱلرَّحۡمَٰنِ
لِبُيُوتِهِمۡ سُقُفٗا مِّن فِضَّةٖ وَمَعَارِجَ عَلَيۡهَا يَظۡهَرُونَ ٣٣

(23) Kuma kamar haka ne, ba Mu taɓa aiko wani mai gargaɗi ba a wata alƙarya a gabaninka sai ‘yan ta-moren cikinsu sun ce: “Lalle mu mun sami iyayenmu a kan wani addini, kuma lalle mu hanyarsu muke kwaikwayo.”

(24) Ya ce (da su: “Yanzu za ku yi koyi da su) ko da na zo muku da abin da ya fi zama shiriya a kan abin da kuka sami iyayenku a kansa?” Suka ce: “Lalle mu masu kafirce wa abin da aka aiko ku da shi ne.”

(25) Sai Muka saka musu da azaba; to duba ka ga yadda ƙarshen masu ƙaryatawa ya kasance

(26) Kuma ka tuna lokacin da Ibrahimu ya ce da Babansa da mutanensa: “Lalle ni ba ruwana da abin da kuke bautawa

(27) “Sai dai wanda Ya halicce ni, to lalle Shi ne Zai shirye ni.”

(28) Ya kuma sanya ta (kalmar Tauhidi ta zama) kalma ce mai wanzuwa a cikin zuri’arsa don (mutanen Makka) su komo (kan hanya).”

(29) A’a, Na jiyar da waɗannan daɗi tare da iyayensu ne har gaskiya ta zo musu da wani manzo mai bayyanawa

(30) Yayin da gaskiyar ta zo musu sai suka ce: “Wannan sihiri ne, kuma lalle mu masu kafirce masa ne.”

(31) Suka kuma ce: “Me ya hana a saukar da wannan Alƙur’ani ga wani babban mutum, daga alƙaryun nan guda biyu?”

(32) Yanzu su ne suke raba rahamar Ubangijinka (ta annabci)? Mu ne Muka raba musu arzikinsu a rayuwar duniya. Muka kuma ɗaukaka darajojin sashinsu a kan sashi, don wani sashin ya riƙi wani sashi mai yi masa hidima. Rahamar Ubangijinka kuma ita ta fi abin da suke tarawa (na duniya)

(33) Ba don kuma kada mutane su zama iri ɗaya ba, da sai Mu sanya wa waɗanda suke kafirce wa (Allah) Mai rahama rufi na azurfa a gidajensu, da kuma matattakala (irinta), da za su riƙa hawa ta kansu

وَلِبُيُوتِهِمْ أَبْوَٰبًا وَسُرُرًا عَلَيْهَا يَتَّكِـُٔونَ ﴿٣٤﴾ وَزُخْرُفًا ۚ وَإِن
كُلُّ ذَٰلِكَ لَمَّا مَتَٰعُ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۚ وَٱلْـَٔاخِرَةُ عِندَ رَبِّكَ
لِلْمُتَّقِينَ ﴿٣٥﴾ وَمَن يَعْشُ عَن ذِكْرِ ٱلرَّحْمَٰنِ نُقَيِّضْ لَهُۥ شَيْطَٰنًا
فَهُوَ لَهُۥ قَرِينٌ ﴿٣٦﴾ وَإِنَّهُمْ لَيَصُدُّونَهُمْ عَنِ ٱلسَّبِيلِ وَيَحْسَبُونَ
أَنَّهُم مُّهْتَدُونَ ﴿٣٧﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَنَا قَالَ يَٰلَيْتَ بَيْنِى وَبَيْنَكَ
بُعْدَ ٱلْمَشْرِقَيْنِ فَبِئْسَ ٱلْقَرِينُ ﴿٣٨﴾ وَلَن يَنفَعَكُمُ ٱلْيَوْمَ
إِذ ظَّلَمْتُمْ أَنَّكُمْ فِى ٱلْعَذَابِ مُشْتَرِكُونَ ﴿٣٩﴾ أَفَأَنتَ تُسْمِعُ
ٱلصُّمَّ أَوْ تَهْدِى ٱلْعُمْىَ وَمَن كَانَ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٤٠﴾ فَإِمَّا
نَذْهَبَنَّ بِكَ فَإِنَّا مِنْهُم مُّنتَقِمُونَ ﴿٤١﴾ أَوْ نُرِيَنَّكَ ٱلَّذِى
وَعَدْنَٰهُمْ فَإِنَّا عَلَيْهِم مُّقْتَدِرُونَ ﴿٤٢﴾ فَٱسْتَمْسِكْ بِٱلَّذِىٓ أُوحِىَ
إِلَيْكَ ۖ إِنَّكَ عَلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٤٣﴾ وَإِنَّهُۥ لَذِكْرٌ لَّكَ وَلِقَوْمِكَ ۖ
وَسَوْفَ تُسْـَٔلُونَ ﴿٤٤﴾ وَسْـَٔلْ مَنْ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ مِن رُّسُلِنَآ
أَجَعَلْنَا مِن دُونِ ٱلرَّحْمَٰنِ ءَالِهَةً يُعْبَدُونَ ﴿٤٥﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا
مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِۦ فَقَالَ إِنِّى رَسُولُ رَبِّ
ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٤٦﴾ فَلَمَّا جَآءَهُم بِـَٔايَٰتِنَآ إِذَا هُم مِّنْهَا يَضْحَكُونَ ﴿٤٧﴾

(34) Kuma (Mu sanya wa) gidajen nasu kofofi da gadaje da za su rika kishingida a kansu

(35) Kuma (Mu sanya musu) zinariya. Duk wadannan ba komai ba ne sai dan jin dadin rayuwar duniya. Lahira kuma a wurin Ubangijinka ta masu takawa ce

(36) Wanda kuwa ya zama mai dundumi game da ambaton (Allah) Mai rahama, to za Mu hada shi da Shaidan ya zama shi ne abokinsa

(37) Lalle kuma su (shaidanun) tabbas suna kange su daga tafarki nagari, su kuma suna zato cewa lalle su shiryayyu ne

(38)Har zuwa lokacin da suka zo mana (wato mutumin da shaidaninsa) sai ya ce: "Ina ma a ce tsakanina da kai akwai nisan gabas da yamma; to tir da aboki irinka."

(39) (Allah Ya ce da su): "A yau tun da kun riga kun yi zalunci zamantowarku tare a cikin azaba ba zai amfane ku ba

(40) Yanzu kai ka iya jiyar da kurame, ko kuma ka iya shiryar da makafi da wanda ya kasance cikin bata mabayyani?

(41) To idan Muka karbi ranka, to lalle Mu Masu yi musu ukuba ne

(42) Ko kuma Muka nuna maka irin abin da muka yi musu alkawarin narko da shi, to lalle Mu Masu iko ne a kansu

(43) To ka rike abin da aka yi maka wahayinsa; lalle kai kana kan hanya madaidaiciya

(44) Kuma lalle shi (Alkur'ani) daukaka ce a gare ka da mutanenka; ba da dadewa ba kuma za a tambaye ku (game da hakkinsa)

(45) Ka tambayi wadanda Muka aiko gabaninka daga manzanninmu, shin Mun sanya wasu ababen bauta da ake bauta musu ba (Allah) Mai rahama ba?

(46) Hakika kuma Mun aiko Musa da ayoyinmu zuwa ga Fir'auna da manyan fadawansa, sai ya ce: "Lalle ni Manzo ne na Ubangijin talikai."

(47) To lokacin da ya zo musu da ayoyinmu sai ga su suna yi musu dariya

وَمَا نُرِيهِم مِّنْ ءَايَةٍ إِلَّا هِيَ أَكْبَرُ مِنْ أُخْتِهَا ۖ وَأَخَذْنَٰهُم
بِٱلْعَذَابِ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿٤٨﴾ وَقَالُوا۟ يَٰٓأَيُّهَ ٱلسَّاحِرُ ٱدْعُ لَنَا
رَبَّكَ بِمَا عَهِدَ عِندَكَ إِنَّنَا لَمُهْتَدُونَ ﴿٤٩﴾ فَلَمَّا كَشَفْنَا
عَنْهُمُ ٱلْعَذَابَ إِذَا هُمْ يَنكُثُونَ ﴿٥٠﴾ وَنَادَىٰ فِرْعَوْنُ فِى قَوْمِهِۦ
قَالَ يَٰقَوْمِ أَلَيْسَ لِى مُلْكُ مِصْرَ وَهَٰذِهِ ٱلْأَنْهَٰرُ تَجْرِى مِن
تَحْتِىٓ ۖ أَفَلَا تُبْصِرُونَ ﴿٥١﴾ أَمْ أَنَا۠ خَيْرٌ مِّنْ هَٰذَا ٱلَّذِى هُوَ مَهِينٌ
وَلَا يَكَادُ يُبِينُ ﴿٥٢﴾ فَلَوْلَآ أُلْقِىَ عَلَيْهِ أَسْوِرَةٌ مِّن ذَهَبٍ أَوْ جَآءَ
مَعَهُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ مُقْتَرِنِينَ ﴿٥٣﴾ فَٱسْتَخَفَّ قَوْمَهُۥ
فَأَطَاعُوهُ ۚ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ قَوْمًا فَٰسِقِينَ ﴿٥٤﴾ فَلَمَّآ ءَاسَفُونَا
ٱنتَقَمْنَا مِنْهُمْ فَأَغْرَقْنَٰهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٥٥﴾ فَجَعَلْنَٰهُمْ
سَلَفًا وَمَثَلًا لِّلْءَاخِرِينَ ﴿٥٦﴾ ۞ وَلَمَّا ضُرِبَ ٱبْنُ مَرْيَمَ مَثَلًا
إِذَا قَوْمُكَ مِنْهُ يَصِدُّونَ ﴿٥٧﴾ وَقَالُوٓا۟ ءَأَٰلِهَتُنَا خَيْرٌ أَمْ
هُوَ ۚ مَا ضَرَبُوهُ لَكَ إِلَّا جَدَلًۢا ۚ بَلْ هُمْ قَوْمٌ خَصِمُونَ ﴿٥٨﴾ إِنْ هُوَ
إِلَّا عَبْدٌ أَنْعَمْنَا عَلَيْهِ وَجَعَلْنَٰهُ مَثَلًا لِّبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿٥٩﴾
وَلَوْ نَشَآءُ لَجَعَلْنَا مِنكُم مَّلَٰٓئِكَةً فِى ٱلْأَرْضِ يَخْلُفُونَ ﴿٦٠﴾

(48) Ba Mu kuma nuna musu wata aya ba sai wadda take ta fi `yar'uwarta girma; Muka kuma kama su da azaba don su dawo (kan hanya)

(49) Suka kuma ce: "Ya kai wannan mai sihiri, ka roƙa mana Ubangijinka da abin da Ya yi maka wahayinsa (Ya yaye mana azaba), lalle mu tabbas za mu shiriya."

(50) To lokacin da Muka yaye musu azabar sai ga su suna warware alƙawari

(51) Fir'auna kuma ya yi shela a cikin mutanensa ya ce: "Ya ku mutanena, yanzu mulkin Misra ba nawa ba ne, kuma ga ƙoramu suna ta kwarara ta ƙarƙashina, ko ba kwa gani ne?

(52) "A'a, ni na fi wannan wulaƙantaccen wanda da ƙyar yake iya bayani

(53) "To me ya hana a saukar masa da warawarai na zinare, ko kuma wasu mala'iku su zo tare da shi suna masu dafa masa baya?"

(54) Sai ya yi wasa da hankalin mutanensa sai suka bi shi. Lalle su sun kasance mutane ne fasiƙai

(55) To lokacin da suka fusata Mu sai Muka saukar musu da uƙuba, Muka nutsar da su ga baki ɗaya

(56) Sai Muka sanya su ja-gaba (wajen hallakarwa), kuma wa'azi ga na baya

(57) Lokacin da kuwa aka buga misali da (Isa) ɗan Maryamu, sai ga mutanenka suna ta annashawa game da shi[1]

(58) Suka kuma ce: "Yanzu ababen bautar mu ne suka fi ko kuwa shi (Isa)?" Ba su buga maka misali da shi ba sai don son jayayya. Ba shakka su dai mutane ne masu tsananin jayayya

(59) Shi (Isa) ba wani ba ne face bawa ne da Muka yi masa ni'ima, Muka kuma sanya shi abin buga misali ga Bani-Isra'ila

(60) Da kuma za Mu ga dama tabbas da Mun sanya mala'iku ne za su maye gurbinku a bayan ƙasa

(1) Watau lokacin da Abdullahi xan Az-Ziba'ara ya ji faxar Allah cewa, waxanda aka bautawa ba Allah ba za su shiga wuta tare da masu bautarsu, sai ya ce, to idan haka ne Annabi Isa ma zai shiga wuta, wannan magana tasa ta faranta wa mushirikai rai sosai.

وَإِنَّهُۥ لَعِلۡمٞ لِّلسَّاعَةِ فَلَا تَمۡتَرُنَّ بِهَا وَٱتَّبِعُونِۚ هَٰذَا صِرَٰطٞ
مُّسۡتَقِيمٞ ٦١ وَلَا يَصُدَّنَّكُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُۖ إِنَّهُۥ لَكُمۡ عَدُوّٞ مُّبِينٞ
٦٢ وَلَمَّا جَآءَ عِيسَىٰ بِٱلۡبَيِّنَٰتِ قَالَ قَدۡ جِئۡتُكُم بِٱلۡحِكۡمَةِ
وَلِأُبَيِّنَ لَكُم بَعۡضَ ٱلَّذِي تَخۡتَلِفُونَ فِيهِۖ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ
٦٣ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ رَبِّي وَرَبُّكُمۡ فَٱعۡبُدُوهُۚ هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ
٦٤ فَٱخۡتَلَفَ ٱلۡأَحۡزَابُ مِنۢ بَيۡنِهِمۡۖ فَوَيۡلٞ لِّلَّذِينَ ظَلَمُواْ
مِنۡ عَذَابِ يَوۡمٍ أَلِيمٖ ٦٥ هَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّا ٱلسَّاعَةَ أَن
تَأۡتِيَهُم بَغۡتَةٗ وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ٦٦ ٱلۡأَخِلَّآءُ يَوۡمَئِذِۭ
بَعۡضُهُمۡ لِبَعۡضٍ عَدُوٌّ إِلَّا ٱلۡمُتَّقِينَ ٦٧ يَٰعِبَادِ لَا خَوۡفٌ
عَلَيۡكُمُ ٱلۡيَوۡمَ وَلَآ أَنتُمۡ تَحۡزَنُونَ ٦٨ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِـَٔايَٰتِنَا
وَكَانُواْ مُسۡلِمِينَ ٦٩ ٱدۡخُلُواْ ٱلۡجَنَّةَ أَنتُمۡ وَأَزۡوَٰجُكُمۡ
تُحۡبَرُونَ ٧٠ يُطَافُ عَلَيۡهِم بِصِحَافٖ مِّن ذَهَبٖ وَأَكۡوَابٖۖ
وَفِيهَا مَا تَشۡتَهِيهِ ٱلۡأَنفُسُ وَتَلَذُّ ٱلۡأَعۡيُنُۖ وَأَنتُمۡ فِيهَا
خَٰلِدُونَ ٧١ وَتِلۡكَ ٱلۡجَنَّةُ ٱلَّتِيٓ أُورِثۡتُمُوهَا بِمَا كُنتُمۡ
تَعۡمَلُونَ ٧٢ لَكُمۡ فِيهَا فَٰكِهَةٞ كَثِيرَةٞ مِّنۡهَا تَأۡكُلُونَ ٧٣

(61) Lalle kuma shi (Isa) alama ce ta zuwan alƙiyama[1], kada ku yi shakka game da ita, kuma ku bi Ni. Wannan ita ce hanya madaidaiciya

(62) Kada kuma Shaiɗan ya kange ku; lalle shi maƙiyi ne mai bayyana (ƙiyyaya) a gare ku

(63) Lokacin da kuma Isa ya zo da hujjoji bayyanannu ya ce: "Haƙiƙa na zo muku da hikima, don kuma in bayyana muku wasu sashin da kuke sassaɓawa cikinsa; to ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku bi ni

(64) "Lalle Allah Shi ne Ubangijina kuma Ubangijinku, sai ku bauta masa. Wannan ita ce hanya madaidaiciya."

(65) Sai ƙungiyoyi suka sassaɓa a tsakaninsu[2]; don haka tsananin azabar yini mai raɗaɗi ya tabbata ga waɗanda suka yi zalunci

(66) Ba abin da suke jira sai alƙiyama kawai ta zo musu kwatsam, alhali ba tare da sun sani ba

(67) Masoya a wannan ranar maƙiyan juna ne sai masu taƙawa kaɗai

(68) Ya ku bayina, babu wani tsoro gare ku a yau, kuma ba za ku yi baƙin ciki ba

(69) (Su ne) waɗanda suka yi imani da ayoyinmu, suka kuma kasance Musulmi

(70) (Za a ce da su): "Ku shiga Aljanna ku da matanku, za a faranta muku rai."

(71) Ana zagayawa tsakaninsu da akusa na zinari da kofuna; a cikinta kuma akwai (duk) abin da rayuka suke sha'awa, idanuwa kuma suke jin daɗin (ganinsu); ku kuma a cikinta madawwama ne

(72) Waccan kuma ita ce Aljannar da aka gadar muku ita saboda abin da kuka kasance kuma aikatawa

(73) A cikinta kuna da `ya`yan itatuwa na marmari masu yawa, daga gare su kuma za ku riƙa ci

(1) Watau lokacin da zai sauko daga sama ta biyu a qarshen zamani, kamar yadda tarin hadisan Annabi ( ) suka tabbatar.

(2) Wasu suka ce shi Allah ne; wasu kuma suka ce xan Allah ne; wasu kuma suka ce shi da mahaifiyarsa duka alloli ne.

إِنَّ ٱلْمُجْرِمِينَ فِى عَذَابِ جَهَنَّمَ خَٰلِدُونَ ﴿٧٤﴾ لَا يُفَتَّرُ عَنْهُمْ وَهُمْ
فِيهِ مُبْلِسُونَ ﴿٧٥﴾ وَمَا ظَلَمْنَٰهُمْ وَلَٰكِن كَانُوا۟ هُمُ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٧٦﴾
وَنَادَوْا۟ يَٰمَٰلِكُ لِيَقْضِ عَلَيْنَا رَبُّكَ ۖ قَالَ إِنَّكُم مَّٰكِثُونَ ﴿٧٧﴾ لَقَدْ
جِئْنَٰكُم بِٱلْحَقِّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَكُمْ لِلْحَقِّ كَٰرِهُونَ ﴿٧٨﴾ أَمْ أَبْرَمُوٓا۟ أَمْرًا
فَإِنَّا مُبْرِمُونَ ﴿٧٩﴾ أَمْ يَحْسَبُونَ أَنَّا لَا نَسْمَعُ سِرَّهُمْ وَنَجْوَىٰهُم ۚ بَلَىٰ
وَرُسُلُنَا لَدَيْهِمْ يَكْتُبُونَ ﴿٨٠﴾ قُلْ إِن كَانَ لِلرَّحْمَٰنِ وَلَدٌ ۖ فَأَنَا۠ أَوَّلُ
ٱلْعَٰبِدِينَ ﴿٨١﴾ سُبْحَٰنَ رَبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ رَبِّ ٱلْعَرْشِ
عَمَّا يَصِفُونَ ﴿٨٢﴾ فَذَرْهُمْ يَخُوضُوا۟ وَيَلْعَبُوا۟ حَتَّىٰ يُلَٰقُوا۟ يَوْمَهُمُ
ٱلَّذِى يُوعَدُونَ ﴿٨٣﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى فِى ٱلسَّمَآءِ إِلَٰهٌ وَفِى ٱلْأَرْضِ
إِلَٰهٌ ۚ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٨٤﴾ وَتَبَارَكَ ٱلَّذِى لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا ۚ وَعِندَهُۥ عِلْمُ ٱلسَّاعَةِ ۚ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ
﴿٨٥﴾ وَلَا يَمْلِكُ ٱلَّذِينَ يَدْعُونَ مِن دُونِهِ ٱلشَّفَٰعَةَ إِلَّا
مَن شَهِدَ بِٱلْحَقِّ وَهُمْ يَعْلَمُونَ ﴿٨٦﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَهُمْ
لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ۖ فَأَنَّىٰ يُؤْفَكُونَ ﴿٨٧﴾ وَقِيلِهِۦ يَٰرَبِّ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ قَوْمٌ
لَّا يُؤْمِنُونَ ﴿٨٨﴾ فَٱصْفَحْ عَنْهُمْ وَقُلْ سَلَٰمٌ ۚ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ﴿٨٩﴾

(74) Lalle masu manyan laifuka suna cikin azabar (wutar) Jahannama suna masu dawwama (75) Ba a yanke musu ita (azabar), su kuwa masu yanke ƙaunar (fita) ne daga cikinta (76) Ba Mu kuwa zalunce su ba, sai dai su ne suka kasance azzalumai (77) Suka kuma yi kiran: "Ya (kai mai tsaron wuta) Maliku, Ubangijinka Ya kashe mu mana!" Ya ce: "Lalle ku masu dawwama ne."

(78) Haƙiƙa Mun zo muku da gaskiya sai dai kuma mafiya yawanku masu ƙin gaskiya ne (79) A'a, sun dai shirya wani makirci ne, Mu ma lalle Masu yin namu shirin ne (80) Ko suna tsammanin cewa Mu ba Ma jin asirinsu da ganawarsu ne? Ba haka ba ne, manzanninmu suna tare da su suna rubutawa(81) Ka ce: "Idan da (Allah) Mai rahama zai zamanto Yana da ɗa, to ni ne farkon masu bauta[1]." (82) Tsarki ya tabbata ga Ubangijin sammai da ƙasa, Ubangiijn Al'arshi game da abin da suke siffantawa (83)Sai ka bar su su yi ta kutse suna wasanni, har su haɗu da ranar da ake alƙawarta musu (84) Shi ne kuma Wanda Yake Abin bauta a cikin sama kuma Abin bauta a ƙasa. Kuma Shi Mai hikima ne, Masani (85) Kuma wanda Yake da mulkin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu alhairansa sun yi yawa, kuma a wurinsa sanin (ranar) alƙiyama yake, wurinsa kuma za a komar da ku (86) Waɗanda kuwa suke bauta wa wani abu ba Shi ba, ba sa mallakar ceto, sai dai waɗanda suka yi Kalmar Shahada ta gaskiya, alhalin suna sane (da ma'anarta) (87) Tabbas kuma da za ka tambaye su, wane ne ya halicce su? Lalle za su ce: "Allah ne;" to ta yaya ake kautar da su? (88) Kuma (sanin) faɗarsa (wato Ma'aiki) cewa: "Ya Ubangiji lalle waɗannan mutane ne da ba sa yin imani," (yana a wurinsa)(89) To ka kawar musu kai, kuma ka ce: "Na kuɓuta (daga haƙƙinku). Don haka ba da daɗewa ba za ku sani."

(1) Watau shi ne farkon masu bauta wa wannan xan, domin kuwa ya zama wani sashi ne na Allah.

Sura Dukhan

سُورَةُ الدُّخَانِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حمٓ ﴿١﴾ وَالْكِتَابِ الْمُبِينِ ﴿٢﴾ إِنَّا أَنزَلْنَاهُ فِي لَيْلَةٍ مُّبَارَكَةٍ
إِنَّا كُنَّا مُنذِرِينَ ﴿٣﴾ فِيهَا يُفْرَقُ كُلُّ أَمْرٍ حَكِيمٍ ﴿٤﴾ أَمْرًا
مِّنْ عِندِنَا إِنَّا كُنَّا مُرْسِلِينَ ﴿٥﴾ رَحْمَةً مِّن رَّبِّكَ إِنَّهُ هُوَ
السَّمِيعُ الْعَلِيمُ ﴿٦﴾ رَبِّ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا
إِن كُنتُم مُّوقِنِينَ ﴿٧﴾ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ يُحْيِي وَيُمِيتُ رَبُّكُمْ
وَرَبُّ آبَائِكُمُ الْأَوَّلِينَ ﴿٨﴾ بَلْ هُمْ فِي شَكٍّ يَلْعَبُونَ ﴿٩﴾
فَارْتَقِبْ يَوْمَ تَأْتِي السَّمَاءُ بِدُخَانٍ مُّبِينٍ ﴿١٠﴾ يَغْشَى النَّاسَ
هَٰذَا عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿١١﴾ رَبَّنَا اكْشِفْ عَنَّا الْعَذَابَ إِنَّا مُؤْمِنُونَ
﴿١٢﴾ أَنَّىٰ لَهُمُ الذِّكْرَىٰ وَقَدْ جَاءَهُمْ رَسُولٌ مُّبِينٌ ﴿١٣﴾ ثُمَّ
تَوَلَّوْا عَنْهُ وَقَالُوا مُعَلَّمٌ مَّجْنُونٌ ﴿١٤﴾ إِنَّا كَاشِفُوا الْعَذَابِ قَلِيلًا
إِنَّكُمْ عَائِدُونَ ﴿١٥﴾ يَوْمَ نَبْطِشُ الْبَطْشَةَ الْكُبْرَىٰ إِنَّا مُنتَقِمُونَ
﴿١٦﴾ * وَلَقَدْ فَتَنَّا قَبْلَهُمْ قَوْمَ فِرْعَوْنَ وَجَاءَهُمْ رَسُولٌ كَرِيمٌ
﴿١٧﴾ أَنْ أَدُّوا إِلَيَّ عِبَادَ اللَّهِ إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿١٨﴾

(1) HA MIM[1] .
(2) Na rantse da Littafi mai bayyanawa (shi ne Alƙur'ani)
(3) Lalle Mu Muka saukar da shi a cikin dare mai albarka[2]. Lalle Mu Mun kasance Masu gargaɗi
(4) A cikinsa ne (daren) ake fasalta kowane tabbataccen al'amari (na wannan shekara)[3]
(5) Al'amari ne (da Muke fasaltawa) daga wurinmu. Lalle Mun kasance Mu ne Masu aikowa (da manzanni)
(6) Don rahama daga Ubangijinka. Lalle shi Mai ji ne, Masani (7) Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu; idan kun kasance masu sakankancewa (8) Babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi, Shi ne Yake rayarwa Yake kuma kashewa; (Shi ne) Ubangijinku kuma Ubangijin iyayenku na farko (9)A'a, su dai suna cikin shakka ne, suna wasanni
(10) Sai ka saurari ranar da sama za ta zo da hayaƙi bayyananne[4] (11) Zai lulluɓe (idanuwan) mutane; wannan azaba ce mai raɗaɗi (12) (Za su ce): "Ya Ubangijinmu, Ka yaye mana wannan azaba, lalle mu masu yin imani ne." (13) Ta ina wa'azi zai amfane su, alhali kuwa haƙiƙa Manzo mai bayani ya zo musu?(14) Sannan suka juya masa baya suka ce: "Ai wani ne ya koya masa, (kuma shi) taɓaɓɓe ne (15) Lalle Mu Masu yaye muku azabar ne ɗan lokaci kaɗan. Lalle (kuma) ku masu komawa ne (16) (Ka tuna) ranar da za Mu damƙe su babbar damƙa[5], lalle Mu Masu sakawa ne (17) Haƙiƙa kuma Mun jarrabi mutanen Fir'auna tun kafin su, kuma Manzo mai karamci ya zo musu (18) (Da cewa): "Ku ba ni bayin Allah (watau Banu Isra'ila); lalle ni Manzo ne amintacce a gare ku

(1) Duba Suratul Baqara aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Shi ne daren Lailatul Qadari. Duba Suratul Qadri.

(3) Watau al'amarin da ya shafi rabon arziqi da tsawon rai da sauran abubuwa da Allah ya qaddara za su faru a wannan shekarar.

(4) Ita ce ranar yaqin Badar lokacin da Allah ya damqi manyan kafiran Makka aka karkashe su.

(5) Shi ne hayaqi da idanuwansu za su riqa nuna musu, shi saboda tsananin yunwa.



وَأَن لَّا تَعْلُوا۟ عَلَى ٱللَّهِ ۖ إِنِّىٓ ءَاتِيكُم بِسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿١٩﴾ وَإِنِّى عُذْتُ
بِرَبِّى وَرَبِّكُمْ أَن تَرْجُمُونِ ﴿٢٠﴾ وَإِن لَّمْ تُؤْمِنُوا۟ لِى فَٱعْتَزِلُونِ ﴿٢١﴾
فَدَعَا رَبَّهُۥٓ أَنَّ هَٰٓؤُلَآءِ قَوْمٌ مُّجْرِمُونَ ﴿٢٢﴾ فَأَسْرِ بِعِبَادِى لَيْلًا إِنَّكُم
مُّتَّبَعُونَ ﴿٢٣﴾ وَٱتْرُكِ ٱلْبَحْرَ رَهْوًا ۖ إِنَّهُمْ جُندٌ مُّغْرَقُونَ ﴿٢٤﴾ كَمْ
تَرَكُوا۟ مِن جَنَّٰتٍ وَعُيُونٍ ﴿٢٥﴾ وَزُرُوعٍ وَمَقَامٍ كَرِيمٍ ﴿٢٦﴾ وَنَعْمَةٍ
كَانُوا۟ فِيهَا فَٰكِهِينَ ﴿٢٧﴾ كَذَٰلِكَ ۖ وَأَوْرَثْنَٰهَا قَوْمًا ءَاخَرِينَ ﴿٢٨﴾ فَمَا
بَكَتْ عَلَيْهِمُ ٱلسَّمَآءُ وَٱلْأَرْضُ وَمَا كَانُوا۟ مُنظَرِينَ ﴿٢٩﴾ وَلَقَدْ
نَجَّيْنَا بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ مِنَ ٱلْعَذَابِ ٱلْمُهِينِ ﴿٣٠﴾ مِن فِرْعَوْنَ ۚ إِنَّهُۥ
كَانَ عَالِيًا مِّنَ ٱلْمُسْرِفِينَ ﴿٣١﴾ وَلَقَدِ ٱخْتَرْنَٰهُمْ عَلَىٰ عِلْمٍ عَلَى
ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٣٢﴾ وَءَاتَيْنَٰهُم مِّنَ ٱلْءَايَٰتِ مَا فِيهِ بَلَٰٓؤٌا۟ مُّبِينٌ ﴿٣٣﴾
إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ لَيَقُولُونَ ﴿٣٤﴾ إِنْ هِىَ إِلَّا مَوْتَتُنَا ٱلْأُولَىٰ وَمَا نَحْنُ
بِمُنشَرِينَ ﴿٣٥﴾ فَأْتُوا۟ بِـَٔابَآئِنَآ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٣٦﴾ أَهُمْ
خَيْرٌ أَمْ قَوْمُ تُبَّعٍ وَٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ ۚ أَهْلَكْنَٰهُمْ ۚ إِنَّهُمْ كَانُوا۟
مُجْرِمِينَ ﴿٣٧﴾ وَمَا خَلَقْنَا ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا لَٰعِبِينَ
﴿٣٨﴾ مَا خَلَقْنَٰهُمَآ إِلَّا بِٱلْحَقِّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٣٩﴾

(19) “Kuma kada ku yi wa Allah girman kai; lalle ni zan kawo muku hujjoji mabayyana
(20) “Kuma lalle ni ina neman tsari na Ubangijina kuma Ubangijinku, don kada ku jefe ni
(21) “Idan kuma ba ku yi imani da ni ba sai ku ƙyale ni.”
(22) Sai ya roƙi Ubangijinsa cewa: “Lalle waɗannan mutane ne masu manyan laifuka.”
(23) Sai (aka ce masa): “Ka tafi da bayina da daddare, lalle ku za a biyo bayanku
(24)“Kuma ka bar kogi a tsaye cak (bayan tsallakewa); lalle su runduna ne da za a nutsar.” (25) Sun bar gonaki da kuma idanuwan ruwa masu yawa (26) Da kuma shuke-shuke da wurin zama mai daraja(27) Da kuma kayan jin daɗi da suka kasance masu ni’imtuwa da su
(28) Kamar haka ne; sai Muka kuma gadar da su ga wasu mutane daban (su ne Banu Isra’ila) (29) Sannan (halittun) sama da na ƙasa ba su yi alhininsu ba, ba su kuma kasance ababen saurara wa ba (30) Haƙiƙa kuma Mun tserar da Banu Isra’ila daga azabar wulaƙanci (31) Daga Fir’auna. Lalle shi ya kasance mai girman kai daga maɓarnata(32) Kuma haƙiƙa Mun fifita su (Banu Isra’ila) bisa saninmu a kan (sauran) talikai(33) Muka kuma ba su wasu ayoyinmu waɗanda a cikinsa akwai jarrabawa mabayyaniya (34) Lalle waɗannan (kafiran Makka) tabbas suna cewa:
(35) “Babu wata mutuwa da za mu yi sai mutuwarmu ta farko, kuma mu ba za a tashe mu ba(36) “To ku zo mana da iyayenmu idan kun kasance masu gaskiya.” (37) Yanzu su ne suka fi ko kuwa mutanen Tubba’u[1] da waɗanda suke a gabaninsu? Duk Mun hallakar da su. Lalle sun kasance masu manyan laifuka (38) Ba Mu kuma halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu don wasa ba(39) Ba Mu halicce su ba sai don gaskiya, sai dai kuma yawancinsu ba su san haka ba

(1) Mutanen Makka sun yarda cewa qabilun Larabawan Himyar da Saba’u waxanda ake kira mutanen Tubba’u na qasar Yaman sun fi su qarfin Mulki da jin daxin duniya.

إِنَّ يَوْمَ ٱلْفَصْلِ مِيقَٰتُهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٤٠﴾ يَوْمَ لَا يُغْنِى مَوْلًى
عَن مَّوْلًى شَيْـًٔا وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿٤١﴾ إِلَّا مَن رَّحِمَ ٱللَّهُ
إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٤٢﴾ إِنَّ شَجَرَتَ ٱلزَّقُّومِ ﴿٤٣﴾ طَعَامُ
ٱلْأَثِيمِ ﴿٤٤﴾ كَٱلْمُهْلِ يَغْلِى فِى ٱلْبُطُونِ ﴿٤٥﴾ كَغَلْىِ
ٱلْحَمِيمِ ﴿٤٦﴾ خُذُوهُ فَٱعْتِلُوهُ إِلَىٰ سَوَآءِ ٱلْجَحِيمِ ﴿٤٧﴾ ثُمَّ
صُبُّوا۟ فَوْقَ رَأْسِهِۦ مِنْ عَذَابِ ٱلْحَمِيمِ ﴿٤٨﴾ ذُقْ إِنَّكَ
أَنتَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْكَرِيمُ ﴿٤٩﴾ إِنَّ هَٰذَا مَا كُنتُم بِهِۦ تَمْتَرُونَ
﴿٥٠﴾ إِنَّ ٱلْمُتَّقِينَ فِى مَقَامٍ أَمِينٍ ﴿٥١﴾ فِى جَنَّٰتٍ وَعُيُونٍ
﴿٥٢﴾ يَلْبَسُونَ مِن سُندُسٍ وَإِسْتَبْرَقٍ مُّتَقَٰبِلِينَ ﴿٥٣﴾
كَذَٰلِكَ وَزَوَّجْنَٰهُم بِحُورٍ عِينٍ ﴿٥٤﴾ يَدْعُونَ فِيهَا بِكُلِّ
فَٰكِهَةٍ ءَامِنِينَ ﴿٥٥﴾ لَا يَذُوقُونَ فِيهَا ٱلْمَوْتَ إِلَّا
ٱلْمَوْتَةَ ٱلْأُولَىٰ ۖ وَوَقَىٰهُمْ عَذَابَ ٱلْجَحِيمِ ﴿٥٦﴾ فَضْلًا مِّن
رَّبِّكَ ۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿٥٧﴾ فَإِنَّمَا يَسَّرْنَٰهُ بِلِسَانِكَ
لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿٥٨﴾ فَٱرْتَقِبْ إِنَّهُم مُّرْتَقِبُونَ ﴿٥٩﴾

سُورَةُ الجَاثِيَةِ

(40) Lalle ranar alkiyama ne lokacin da aka kayyade musu gaba daya(41) Ranar da wani masoyi ba zai amfana wa masoyinsa komai ba, su kuma ba za a taimaka musu ba(42) Sai fa wanda Allah Ya ji kan sa. Lalle Shi ne Mabuwayi, Mai rahama
(43) Lalle itaciyar Zakkumu
(44) Abincin mai babban zunubi ce(45) (Kuma) kamar narkakkiyar darma, tana tafarfasa a cikin ciki
(46) Kamar tafasar ruwan zafi
(47) (Za a ce da mala'iku): "Ku kama shi sannan ku ja shi tsakiyar wutar Jahima
(48) "Sannan ku kwarara azabar ruwan zafi a tsakiyar kansa."
(49) (Sai a ce da shi): "Dandana, lalle kai din nan kai babban mutum ne mai daraja[1]
(50) (Za a ce da kafirai): "Lalle wannan ne abin da kuka kasance kuna shakkar sa."
(51) Lalle masu takawa suna cikin wani amintaccen wuri
(52) Cikin lambuna da idanuwan ruwa
(53) Suna saye da tufafi na alharini mai shara-shara da mai kauri suna fuskantar juna
(54) Kamar haka ne, Muka kuma aura musu ('yan matan) Hurul-Ini
(55) A cikinta (Aljannar) suna kiran a kawo musu duk wani kayan marmari, suna cikin aminci
(56) Ba za su dandani wata mutuwa a cikinta ba sai dai mutuwar farko; Ya kuma tserar da su daga azabar wutar Jahima
(57) (Wannan) falala ce daga Ubangijinka. Wannan shi ne babban rabo
(58) To kawai Mun saukake shi ne (wato Alkur'ani) da harshenka, don su wa'azantu
(59) To ka saurara, lalle su ma masu sauraro ne

(1) Watau kamar yadda yake xaukar kansa a duniya. Ana faxa masa haka cikin izgili da ba'a.

Sura Jasiya

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

حمٓ ﴿١﴾ تَنزِيلُ ٱلْكِتَٰبِ مِنَ ٱللَّهِ ٱلْعَزِيزِ ٱلْحَكِيمِ ﴿٢﴾ إِنَّ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ لَءَايَٰتٍ لِّلْمُؤْمِنِينَ ﴿٣﴾ وَفِى خَلْقِكُمْ وَمَا يَبُثُّ مِن دَآبَّةٍ ءَايَٰتٌ
لِّقَوْمٍ يُوقِنُونَ ﴿٤﴾ وَٱخْتِلَٰفِ ٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ وَمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ
مِن رِّزْقٍ فَأَحْيَا بِهِ ٱلْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا وَتَصْرِيفِ ٱلرِّيَٰحِ ءَايَٰتٌ لِّقَوْمٍ
يَعْقِلُونَ ﴿٥﴾ تِلْكَ ءَايَٰتُ ٱللَّهِ نَتْلُوهَا عَلَيْكَ بِٱلْحَقِّ ۖ فَبِأَىِّ حَدِيثٍۭ بَعْدَ
ٱللَّهِ وَءَايَٰتِهِۦ يُؤْمِنُونَ ﴿٦﴾ وَيْلٌ لِّكُلِّ أَفَّاكٍ أَثِيمٍ ﴿٧﴾ يَسْمَعُ ءَايَٰتِ
ٱللَّهِ تُتْلَىٰ عَلَيْهِ ثُمَّ يُصِرُّ مُسْتَكْبِرًا كَأَن لَّمْ يَسْمَعْهَا ۖ فَبَشِّرْهُ بِعَذَابٍ أَلِيمٍ
﴿٨﴾ وَإِذَا عَلِمَ مِنْ ءَايَٰتِنَا شَيْـًٔا ٱتَّخَذَهَا هُزُوًا ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ
مُّهِينٌ ﴿٩﴾ مِّن وَرَآئِهِمْ جَهَنَّمُ ۖ وَلَا يُغْنِى عَنْهُم مَّا كَسَبُوا۟ شَيْـًٔا
وَلَا مَا ٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَوْلِيَآءَ ۖ وَلَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿١٠﴾ هَٰذَا
هُدًى ۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمْ لَهُمْ عَذَابٌ مِّن رِّجْزٍ أَلِيمٌ ﴿١١﴾
* ٱللَّهُ ٱلَّذِى سَخَّرَ لَكُمُ ٱلْبَحْرَ لِتَجْرِىَ ٱلْفُلْكُ فِيهِ بِأَمْرِهِۦ وَلِتَبْتَغُوا۟
مِن فَضْلِهِۦ وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿١٢﴾ وَسَخَّرَ لَكُم مَّا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى
ٱلْأَرْضِ جَمِيعًا مِّنْهُ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ﴿١٣﴾

(1) HA MIM[1] .
(2) Saukar da Alkur'ani daga Allah ne Mabuwayi, Mai hikima
(3) Lalle a cikin sammai da ƙasa tabbas akwai ayoyi ga muminai
(4) A cikin halittarku ma da abin da Yake bazawa na dabbobi, akwai ayoyi ga mutane masu sakankancewa
(5) Da kuma sassaɓawar dare da yini da abin da Ya saukar daga sama na arziki, sai Ya raya ƙasa da shi bayan mutuwarta, da kuma jujjuyawar iska, akwai ayoyi ga mutanen da suke hankalta
(6) Waɗannan su ne ayoyin Allah da Muke karanta maka su da gaskiya; to da wane zance ne za su yi imani bayan (zancen) Allah da ayoyinsa?
(7) Tsananin azaba ya tabbata ga duk wani maƙaryaci mai yawan saɓo
(8) Yana jin ana karanta masa ayoyin Allah, sai ya doge yana mai girman kai kamar bai ji su ba; to ka yi masa albishir da azaba mai raɗaɗi
(9) Idan kuma ya san wani abu daga ayoyinmu sai ya ɗauke su abin yi wa izgili. Waɗannan suna da wata azaba mai wulaƙantarwa
(10) A gabansu akwai (wutar) Jahannama, kuma abin da suka tsuwurwurta (na dukiya da waninta), da abubuwan da suka riƙa majiɓinta ba Allah ba, (duk) ba za su amfana musu komai ba; suna kuma da (sakamakon) azaba mai girma
(11) Wannan (Alkur'ani) shiriya ne; waɗanda kuwa suka kafirce da ayoyin Ubangijinsu, suna da (sakamakon) wata mummunar azaba mai raɗaɗi
(12) Allah ne wanda Ya hore muku kogi don jiragen ruwa su riƙa gudu a cikinsa da umarninsa, don kuma ku nema daga falalarsa don kuma ku gode
(13) Ya kuma hore muku abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa gaba ɗayansu daga gare Shi. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutanen da suke yin tunani

(1) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8.

قُل لِّلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ يَغْفِرُوا۟ لِلَّذِينَ لَا يَرْجُونَ أَيَّامَ ٱللَّهِ لِيَجْزِىَ
قَوْمًۢا بِمَا كَانُوا۟ يَكْسِبُونَ ﴿١٤﴾ مَنْ عَمِلَ صَٰلِحًا فَلِنَفْسِهِۦ ۖ
وَمَنْ أَسَآءَ فَعَلَيْهَا ۖ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُمْ تُرْجَعُونَ ﴿١٥﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا
بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحُكْمَ وَٱلنُّبُوَّةَ وَرَزَقْنَٰهُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ
وَفَضَّلْنَٰهُمْ عَلَى ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٦﴾ وَءَاتَيْنَٰهُم بَيِّنَٰتٍ مِّنَ ٱلْأَمْرِ ۖ
فَمَا ٱخْتَلَفُوٓا۟ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلْعِلْمُ بَغْيًۢا بَيْنَهُمْ ۚ إِنَّ رَبَّكَ
يَقْضِى بَيْنَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُوا۟ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ
﴿١٧﴾ ثُمَّ جَعَلْنَٰكَ عَلَىٰ شَرِيعَةٍ مِّنَ ٱلْأَمْرِ فَٱتَّبِعْهَا وَلَا تَتَّبِعْ
أَهْوَآءَ ٱلَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٨﴾ إِنَّهُمْ لَن يُغْنُوا۟ عَنكَ مِنَ ٱللَّهِ
شَيْـًٔا ۚ وَإِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ بَعْضُهُمْ أَوْلِيَآءُ بَعْضٍ ۖ وَٱللَّهُ وَلِىُّ ٱلْمُتَّقِينَ
﴿١٩﴾ هَٰذَا بَصَآئِرُ لِلنَّاسِ وَهُدًى وَرَحْمَةٌ لِّقَوْمٍ يُوقِنُونَ ﴿٢٠﴾
أَمْ حَسِبَ ٱلَّذِينَ ٱجْتَرَحُوا۟ ٱلسَّيِّـَٔاتِ أَن نَّجْعَلَهُمْ كَٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَوَآءً مَّحْيَاهُمْ وَمَمَاتُهُمْ ۚ سَآءَ
مَا يَحْكُمُونَ ﴿٢١﴾ وَخَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ بِٱلْحَقِّ
وَلِتُجْزَىٰ كُلُّ نَفْسٍۭ بِمَا كَسَبَتْ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿٢٢﴾

(14) Ka ce da waɗanda suka yi imani su yi gafara ga waɗanda ba su damu da ni'imomi ko musibu na Allah ba[1], don Ya saka wa mutane game da irin abin da suka kasance suna aikatawa

(15) Duk wanda ya yi aiki nagari to kansa ya yi wa; wanda kuma duk ya munana to a kansa; sannan wurin Ubangijinku ne kawai za a mayar da ku

(16) Haƙiƙa kuma Mun bai wa Banu Isra'ila littafin (Attaura) da hukunci da annabta. Muka kuma arzuta su da tsarkakan (abubuwa), kuma Muka fifita su a kan talikai

(17) Muka kuma kawo musu (hujjoji) mabayyana na addini; to ba su sassaɓa ba, sai bayan da ilimi ya zo musu don hassada a tsakaninsu. Lalle Ubangijinka zai yi hukunci a tsakaninsu a ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna yin saɓani cikinsa

(18) Sannan Muka sanya ka a kan wata shari'a ta addini, to sai ka bi ta, kada kuma ka bi soye-soyen zukatan waɗanda ba sa sanin (gaskiya)

(19) Lalle su ba za su maganta maka komai ba daga Allah. Kuma lalle azzalumai sashinsu masoya sashi ne; Allah kuwa Shi ne Majiɓincin al'amarin masu taƙawa

(20) Wannan (Alƙur'ani) izina ne ga mutane da shiriya da rahama ga mutanen da suke sakankancewa

(21) Yanzu waɗanda suka aikata munanan (ayyuka) suna tsammanin za Mu sanya su ne kamar waɗanda suka yi imani suka kuma yi kyawawan ayyuka, ya zamana rayuwarsu ta duniya da mutuwarsu sun zama daidai? Abin da suke hukuntawa ya munana

(22) Allah kuma Ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya, don kuma a saka wa kowane rai irin abin da ya aikata, alhali kuma su ba za a zalunce su ba

(1) Watau domin Allah zai saka wa bayinsa muminai masu haquri.

أَفَرَءَيْتَ مَنِ ٱتَّخَذَ إِلَٰهَهُۥ هَوَىٰهُ وَأَضَلَّهُ ٱللَّهُ عَلَىٰ عِلْمٍ وَخَتَمَ عَلَىٰ سَمْعِهِۦ
وَقَلْبِهِۦ وَجَعَلَ عَلَىٰ بَصَرِهِۦ غِشَٰوَةً فَمَن يَهْدِيهِ مِنۢ بَعْدِ ٱللَّهِ ۚ أَفَلَا
تَذَكَّرُونَ ﴿٢٣﴾ وَقَالُوا۟ مَا هِىَ إِلَّا حَيَاتُنَا ٱلدُّنْيَا نَمُوتُ وَنَحْيَا وَمَا يُهْلِكُنَآ
إِلَّا ٱلدَّهْرُ ۚ وَمَا لَهُم بِذَٰلِكَ مِنْ عِلْمٍ ۖ إِنْ هُمْ إِلَّا يَظُنُّونَ ﴿٢٤﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ
عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٍ مَّا كَانَ حُجَّتَهُمْ إِلَّآ أَن قَالُوا۟ ٱئْتُوا۟ بِـَٔابَآئِنَآ إِن
كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٢٥﴾ قُلِ ٱللَّهُ يُحْيِيكُمْ ثُمَّ يُمِيتُكُمْ ثُمَّ يَجْمَعُكُمْ إِلَىٰ
يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ لَا رَيْبَ فِيهِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٢٦﴾ وَلِلَّهِ مُلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ وَيَوْمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يَوْمَئِذٍ يَخْسَرُ ٱلْمُبْطِلُونَ ﴿٢٧﴾
وَتَرَىٰ كُلَّ أُمَّةٍ جَاثِيَةً ۚ كُلُّ أُمَّةٍ تُدْعَىٰٓ إِلَىٰ كِتَٰبِهَا ٱلْيَوْمَ تُجْزَوْنَ مَا كُنتُمْ
تَعْمَلُونَ ﴿٢٨﴾ هَٰذَا كِتَٰبُنَا يَنطِقُ عَلَيْكُم بِٱلْحَقِّ ۚ إِنَّا كُنَّا نَسْتَنسِخُ
مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٢٩﴾ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
فَيُدْخِلُهُمْ رَبُّهُمْ فِى رَحْمَتِهِۦ ۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْمُبِينُ ﴿٣٠﴾ وَأَمَّا
ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ أَفَلَمْ تَكُنْ ءَايَٰتِى تُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ فَٱسْتَكْبَرْتُمْ وَكُنتُمْ قَوْمًا
مُّجْرِمِينَ ﴿٣١﴾ وَإِذَا قِيلَ إِنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ وَٱلسَّاعَةُ لَا رَيْبَ فِيهَا
قُلْتُم مَّا نَدْرِى مَا ٱلسَّاعَةُ إِن نَّظُنُّ إِلَّا ظَنًّا وَمَا نَحْنُ بِمُسْتَيْقِنِينَ ﴿٣٢﴾

(23) Shin kuwa ka ga wanda ya ɗauki son zuciyarsa (shi ne) abin bautarsa, Allah kuwa Ya ɓatar da shi a kan yana sane[1], Ya kuma rufe jinsa da zuciyarsa, kuma Ya sanya yana a kan ganinsa, to wane ne zai shiryar da shi in ba Allah ba? Me ya sa ba kwa wa'azantuwa?

(24) Suka kuma ce: "Ai ba wata (rayuwa) sai rayuwarmu ta duniya, da za mu mutu, kuma mu rayu (watau 'ya'yansu)[2], ba kuwa wani abu da yake hallaka mu sai juyin zamani". Alhali kuwa ba su da wani sani game da wannan; ba abin da suke yi sai zato

(25) Idan kuma ana karanta musu ayoyinmu mabayyana, ba su da wata hujja sai kawai su ce: "Ku zo da iyayenmu idan kun kasance masu gaskiya."

(26) Ka ce: "Allah ne zai raya ku sannan ya kashe ku sannan ya tara ku a ranar alƙiyama wadda babu kokwanto game da ita, sai dai kuma yawancin mutane ba sa sanin (haka)."

(27) Mulkin sammai da ƙasa kuma na Allah ne. Kuma ranar da alƙiyama za ta tashi, a wannan ranar maɓarnata za su yi asara

(28) Za kuma ka ga kowace al'umma a durƙushe, kowace al'umma ana kiran ta zuwa ga littafinta, a wannan rana ne za a saka muku abin da kuka kasance kuna aikatawa(29) (Za a ce da su): "Wannan Littafinmu ne da yake yi muku furuci da gaskiya[3]. Lalle Mu mun kasance Muna rubuta abin da kuka kasance kuna aikatawa[4]."(30) To amma waɗanda suka yi imani suka yi ayyuka nagari, to Ubangijinsu zai shigar da su cikin rahamarsa. Wannan shi ne rabo mabayyani(31) Amma kuma waɗanda suka kafirce (za a ce da su): "Yanzu ashe ayoyina ba su kasance ana karanta muku su ba, sai kuka yi girman kai, kuka kasance mutane masu manyan laifuka?"(32) Idan kuma aka ce, lalle alƙawarin Allah gaskiya ne, alƙiyama kuma babu kokwanto a game da ita kukan ce: "Mu ba mu da sanin mece ce ma alƙiyama, mu ba abin da muke tsammani (game da ita) sai zato, mu kuma ba mu da tabbas."

(1) Watau ya vatar da shi bayan ilimi ya zo masa, saboda Allah ya san cewa ya cancanci vata.

(2) Watau bayan sun mutu 'ya'yansu za su ci gaba da rayuwa.

(3) Watau littafin da mala'iku suka rubuta na ayyukansu yana ba da shaida a kansu da tsantsar gaskiya.

(4) Domin Allah ne da kansa ya umarci waxannan mala'ikun su riqa rubuta ayyukan mutane a duniya.


وَبَدَا لَهُمْ سَيِّـَٔاتُ مَا عَمِلُوا۟ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُوا۟ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ
﴿٣٣﴾ وَقِيلَ ٱلْيَوْمَ نَنسَىٰكُمْ كَمَا نَسِيتُمْ لِقَآءَ يَوْمِكُمْ هَٰذَا وَمَأْوَىٰكُمُ ٱلنَّارُ
وَمَا لَكُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿٣٤﴾ ذَٰلِكُم بِأَنَّكُمُ ٱتَّخَذْتُمْ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ هُزُوًا
وَغَرَّتْكُمُ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا ۚ فَٱلْيَوْمَ لَا يُخْرَجُونَ مِنْهَا وَلَا هُمْ يُسْتَعْتَبُونَ
﴿٣٥﴾ فَلِلَّهِ ٱلْحَمْدُ رَبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَرَبِّ ٱلْأَرْضِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٣٦﴾
وَلَهُ ٱلْكِبْرِيَآءُ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٣٧﴾

سُورَةُ الأَحْقَافِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

حمٓ ﴿١﴾ تَنزِيلُ ٱلْكِتَٰبِ مِنَ ٱللَّهِ ٱلْعَزِيزِ ٱلْحَكِيمِ ﴿٢﴾ مَا خَلَقْنَا
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَآ إِلَّا بِٱلْحَقِّ وَأَجَلٍ مُّسَمًّى ۚ وَٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ عَمَّآ أُنذِرُوا۟ مُعْرِضُونَ ﴿٣﴾ قُلْ أَرَءَيْتُم مَّا تَدْعُونَ مِن
دُونِ ٱللَّهِ أَرُونِى مَاذَا خَلَقُوا۟ مِنَ ٱلْأَرْضِ أَمْ لَهُمْ شِرْكٌ فِى
ٱلسَّمَٰوَٰتِ ۖ ٱئْتُونِى بِكِتَٰبٍ مِّن قَبْلِ هَٰذَآ أَوْ أَثَٰرَةٍ مِّنْ عِلْمٍ إِن كُنتُمْ
صَٰدِقِينَ ﴿٤﴾ وَمَنْ أَضَلُّ مِمَّن يَدْعُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَن
لَّا يَسْتَجِيبُ لَهُۥٓ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ وَهُمْ عَن دُعَآئِهِمْ غَٰفِلُونَ ﴿٥﴾

(33) Kuma irin munanan ayyukan da suka aikata suka bayyana a gare su, kuma abin da suka kasance suna yi wa izgili ya saukar musu
(34) Aka kuma ce: “A yau za Mu manta da ku[1] kamar yadda kuka manta haduwarku da wannan rana taku, makomarku kuma wuta ce, kuma ba ku da wasu mataimaka
(35) “Wannan kuwa saboda lalle kun ɗauki ayoyin Allah abin yi wa izgili, rayuwar duniya kuma ta ruɗe ku.” To a yau ba za a fitar da su daga cikinta ba, kuma su ba za a nemi su kawo hanzarinsu ba
(36) To yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin sammai kuma Ubangijin ƙasa, Ubangijin talikai
(37) Girma nasa ne a cikin sammai da ƙasa, kuma Shi ne Mabuwayi, Mai hikima

Sura Ahkaf

(1) HA MIM[2] .
(2) Saukar da Alƙur’ani daga Allah ne Mabuwayi, Mai hikima.
(3) Ba Mu halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu ba sai don gaskiya da kuma (zuwa) wani lokaci ƙayyadajje. Waɗanda kuwa suka kafirta masu bijire wa abin da aka yi musu gargaɗi da shi ne
(4) Ka ce: “Shin kun ga abin da kuke bauta wa ba Allah ba, ku nuna min abin da suka halitta na ƙasa, ko kuwa suna da tarayya ne a (halittar) sammai; ku kawo mini wani littafi da yake gabanin wannan (Alƙur’anin), ko kuma wani ɓirɓishi na ilimi idan kun kasance masu gaskiya.”
(5) Wane ne ya fi ɓata fiye da wanda yake bauta wa wani ba Allah ba, wanda ba zai amsa masa ba har zuwa ranar alƙiyama, kuma su (ababen bautar) rafkanannu ne game da bautar da suke yi musu?

(1) Watau zai bar su a cikin wuta ya yi watsi da su, sakamakon mantawa da suka yi da wannan ranar.

(2) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8.

وَإِذَا حُشِرَ ٱلنَّاسُ كَانُوا۟ لَهُمْ أَعْدَآءً وَكَانُوا۟ بِعِبَادَتِهِمْ كَٰفِرِينَ ﴿٦﴾ وَإِذَا
تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٍ قَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لِلْحَقِّ لَمَّا جَآءَهُمْ هَٰذَا
سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿٧﴾ أَمْ يَقُولُونَ ٱفْتَرَىٰهُ ۖ قُلْ إِنِ ٱفْتَرَيْتُهُۥ فَلَا تَمْلِكُونَ
لِى مِنَ ٱللَّهِ شَيْـًٔا ۖ هُوَ أَعْلَمُ بِمَا تُفِيضُونَ فِيهِ ۖ كَفَىٰ بِهِۦ شَهِيدًۢا بَيْنِى
وَبَيْنَكُمْ ۖ وَهُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٨﴾ قُلْ مَا كُنتُ بِدْعًا مِّنَ ٱلرُّسُلِ
وَمَآ أَدْرِى مَا يُفْعَلُ بِى وَلَا بِكُمْ ۖ إِنْ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ إِلَىَّ وَمَآ أَنَا۠
إِلَّا نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿٩﴾ قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِن كَانَ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ وَكَفَرْتُم بِهِۦ
وَشَهِدَ شَاهِدٌ مِّنۢ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ عَلَىٰ مِثْلِهِۦ فَـَٔامَنَ وَٱسْتَكْبَرْتُمْ ۖ
إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٠﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟
لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَوْ كَانَ خَيْرًا مَّا سَبَقُونَآ إِلَيْهِ ۚ وَإِذْ لَمْ يَهْتَدُوا۟ بِهِۦ
فَسَيَقُولُونَ هَٰذَآ إِفْكٌ قَدِيمٌ ﴿١١﴾ وَمِن قَبْلِهِۦ كِتَٰبُ مُوسَىٰٓ
إِمَامًا وَرَحْمَةً ۚ وَهَٰذَا كِتَٰبٌ مُّصَدِّقٌ لِّسَانًا عَرَبِيًّا لِّيُنذِرَ
ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ وَبُشْرَىٰ لِلْمُحْسِنِينَ ﴿١٢﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ قَالُوا۟ رَبُّنَا
ٱللَّهُ ثُمَّ ٱسْتَقَٰمُوا۟ فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿١٣﴾
أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ خَٰلِدِينَ فِيهَا جَزَآءًۢ بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٤﴾

(6) Idan kuma aka tashi mutane (ababen bautar) za su kasance abokan gabarsu, kuma su zamo masu musanta bautar tasu

(7) Idan kuma an karanta musu ayoyinmu bayyanannu sai waɗanda suka kafirce wa gaskiya lokacin da ta zo musu su ce: “Wannan sihiri ne mabayyani.”

(8) A’a, cewa dai suka yi: “Kagar sa ya yi.” Ka ce: “Idan har na ƙage shi ne to ba za ku amfana min komai ba game da Allah; Shi ne Ya fi sanin abin da kuke kutsawa cikinsa[1]; Shi Ya isa Mai shaida tsakanina da ku; kuma Shi ne Mai gafara, Mai rahama.”

(9) Ka ce: “Ba ni ne farau ba daga manzanni[2], kuma ba ni da sanin abin da za a yi min da abin da za a yi muku; ni ba abin da nake bi sai abin da ake yiwo min wahayinsa, kuma ni ba wani ba ne face mai gargaɗi mai bayyanawa.”

(10) Ka ce: “Ku ba ni labari, idan (Alƙur’ani) ya kasance daga wurin Allah yake, kuka kuma kafirce masa, kuma wani mai shaida daga Banu Isra’ila ya ba da shaida a kan irinsa[3], sai ya yi imani (da shi) ku kuma kuka yi girman kai; to lalle Allah ba Ya shiryar da mutane azzalumai.”

(11) Waɗanda kuma suka kafirce suka ce wa waɗanda suka yi imani: “Da (addinin) ya kasance alheri ne, da su ba su riga mu zuwa gare shi ba.” To tunda kuwa ba su shiriya da shi ba, to za su riƙa cewa: “Wannan ƙarya ce daɗaɗɗiya.”

(12) A gabaninsa kuwa akwai littafin Musa wanda yake jagora ne da rahama. Wannan littafin kuma mai gaskata (na gabaninsa) ne a harshen Larabci, don ya gargaɗi waɗanda suka kafirta da kuma yin albishir ga masu kyautatawa

(13) Lalle waɗanda suka ce: “Allah ne Ubangijinmu”, sannan suka tsaya kyam, to babu wani tsoro a gare su, kuma su ba za su yi baƙin ciki ba

(14) Waɗannan su ne ‘yan Aljanna madawwama a cikinta don sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa

(1) Watau na saqon Alqur’ani da saqon Manzon Allah ( ).

(2) Watau ba shi ne na farko ba da Allah ( ) ya aiko da manzanci ballantana har a riqa mamaki haka.

(3) Watau ya shaida da ingancinsa, duba da abin da ya zo na bayaninsa a cikin littafin Attaura.

وَوَصَّيْنَا ٱلْإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيْهِ إِحْسَٰنًا ۖ حَمَلَتْهُ أُمُّهُۥ كُرْهًا وَوَضَعَتْهُ
كُرْهًا ۖ وَحَمْلُهُۥ وَفِصَٰلُهُۥ ثَلَٰثُونَ شَهْرًا ۚ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ أَشُدَّهُۥ وَبَلَغَ
أَرْبَعِينَ سَنَةً قَالَ رَبِّ أَوْزِعْنِىٓ أَنْ أَشْكُرَ نِعْمَتَكَ ٱلَّتِىٓ أَنْعَمْتَ
عَلَىَّ وَعَلَىٰ وَٰلِدَىَّ وَأَنْ أَعْمَلَ صَٰلِحًا تَرْضَىٰهُ وَأَصْلِحْ لِى فِى ذُرِّيَّتِىٓ ۖ
إِنِّى تُبْتُ إِلَيْكَ وَإِنِّى مِنَ ٱلْمُسْلِمِينَ ﴿١٥﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ نَتَقَبَّلُ
عَنْهُمْ أَحْسَنَ مَا عَمِلُوا۟ وَنَتَجَاوَزُ عَن سَيِّـَٔاتِهِمْ فِىٓ أَصْحَٰبِ
ٱلْجَنَّةِ ۖ وَعْدَ ٱلصِّدْقِ ٱلَّذِى كَانُوا۟ يُوعَدُونَ ﴿١٦﴾ وَٱلَّذِى قَالَ
لِوَٰلِدَيْهِ أُفٍّ لَّكُمَآ أَتَعِدَانِنِىٓ أَنْ أُخْرَجَ وَقَدْ خَلَتِ ٱلْقُرُونُ مِن
قَبْلِى وَهُمَا يَسْتَغِيثَانِ ٱللَّهَ وَيْلَكَ ءَامِنْ إِنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ فَيَقُولُ
مَا هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿١٧﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ حَقَّ عَلَيْهِمُ ٱلْقَوْلُ
فِىٓ أُمَمٍ قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِهِم مِّنَ ٱلْجِنِّ وَٱلْإِنسِ ۖ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ خَٰسِرِينَ
﴿١٨﴾ وَلِكُلٍّ دَرَجَٰتٌ مِّمَّا عَمِلُوا۟ ۖ وَلِيُوَفِّيَهُمْ أَعْمَٰلَهُمْ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ
﴿١٩﴾ وَيَوْمَ يُعْرَضُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ عَلَى ٱلنَّارِ أَذْهَبْتُمْ طَيِّبَٰتِكُمْ فِى حَيَاتِكُمُ
ٱلدُّنْيَا وَٱسْتَمْتَعْتُم بِهَا ۖ فَٱلْيَوْمَ تُجْزَوْنَ عَذَابَ ٱلْهُونِ بِمَا كُنتُمْ
تَسْتَكْبِرُونَ فِى ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ وَبِمَا كُنتُمْ تَفْسُقُونَ ﴿٢٠﴾

(15) Kuma Mun yi wa mutum wasiyya da kyautata wa mahaifansa; mahaifiyarsa ta ɗauki cikinsa a wahalce, ta kuma haife shi a wahalce; ɗaukan cikinsa da yaye shi kuma wata talatin ne, har lokacin da ya cika ƙarfinsa ya kai shekara arba'in ya ce: "Ya Ubangijina, Ka kimsa min yadda zan gode wa ni'imarka, wadda Ka ni'imta ni da ita da kuma mahaifana, kuma (Ka ba ni iko) in yi aiki nagari wanda za Ka yarda da shi, kuma Ka kyautata min zurriyata; lalle ni na tuba a gare Ka, kuma lalle ni ina daga cikin Musulmi."

(16) Waɗannan su ne waɗanda Muke karɓar mafi kyan abin da suka aikata, kuma Muke yafe musu munanan ayyukansu, suna cikin 'yan Aljanna; (wannan) alƙawari ne na gaskiya wanda suka kasance ana yi musu alƙawarinsa (a duniya)


(17) Wanda kuma ya ce da mahaifansa: "Tir da ku, yanzu kwa riƙa yi min alƙawarin za a fito da ni (daga ƙabarina), alhali kuwa tuni wasu al'ummu sun shuɗe gabanina?" Su kuma suna ta roƙon Allah da cewa: "Kaiconka, ka yi imani mana, lalle alƙawarin Allah tabbatacce ne," sannan ya ce: "Wannan ba wani abu ba ne face tatsuniyoyin mutanen farko!"

(18) Waɗannan su ne waɗanda kalmar azaba ta tabbata a kansu cikin al'ummun da suka gabace su na aljannu da mutane; lalle su sun kasance asararru

(19) Kuma kowane yana da darajoji (na sakamakon) abin da suka aikata; don kuma tabbas zai cika musu sakamakon ayyukansu, ba kuma za a zalunce su ba

(20) (Ka tuna) kuma ranar da za a bijiro da waɗanda suka kafirta a gaban wuta, (a ce da su): "Kun tafiyar da jin daɗinku a rayuwarku ta duniya, kuma kun more ta, to a yau za a saka muku da azabar wulaƙanci saboda kun kasance kuna girman kai a bayan ƙasa ba da wata hujja ba, saboda kuma kun kasance kuna yin fasiƙanci."




* وَٱذۡكُرۡ أَخَا عَادٍ إِذۡ أَنذَرَ قَوۡمَهُۥ بِٱلۡأَحۡقَافِ وَقَدۡ خَلَتِ ٱلنُّذُرُ
مِنۢ بَيۡنِ يَدَيۡهِ وَمِنۡ خَلۡفِهِۦٓ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّا ٱللَّهَ إِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ
عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٖ ٢١ قَالُوٓاْ أَجِئۡتَنَا لِتَأۡفِكَنَا عَنۡ ءَالِهَتِنَا فَأۡتِنَا
بِمَا تَعِدُنَآ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٢٢ قَالَ إِنَّمَا ٱلۡعِلۡمُ عِندَ ٱللَّهِ
وَأُبَلِّغُكُم مَّآ أُرۡسِلۡتُ بِهِۦ وَلَٰكِنِّيٓ أَرَىٰكُمۡ قَوۡمٗا تَجۡهَلُونَ ٢٣ فَلَمَّا
رَأَوۡهُ عَارِضٗا مُّسۡتَقۡبِلَ أَوۡدِيَتِهِمۡ قَالُواْ هَٰذَا عَارِضٞ مُّمۡطِرُنَاۚ
بَلۡ هُوَ مَا ٱسۡتَعۡجَلۡتُم بِهِۦۖ رِيحٞ فِيهَا عَذَابٌ أَلِيمٞ ٢٤ تُدَمِّرُ كُلَّ
شَيۡءِۭ بِأَمۡرِ رَبِّهَا فَأَصۡبَحُواْ لَا يُرَىٰٓ إِلَّا مَسَٰكِنُهُمۡۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي
ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ٢٥ وَلَقَدۡ مَكَّنَّٰهُمۡ فِيمَآ إِن مَّكَّنَّٰكُمۡ فِيهِ
وَجَعَلۡنَا لَهُمۡ سَمۡعٗا وَأَبۡصَٰرٗا وَأَفۡـِٔدَةٗ فَمَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُمۡ سَمۡعُهُمۡ
وَلَآ أَبۡصَٰرُهُمۡ وَلَآ أَفۡـِٔدَتُهُم مِّن شَيۡءٍ إِذۡ كَانُواْ يَجۡحَدُونَ بِـَٔايَٰتِ
ٱللَّهِ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٢٦ وَلَقَدۡ أَهۡلَكۡنَا
مَا حَوۡلَكُم مِّنَ ٱلۡقُرَىٰ وَصَرَّفۡنَا ٱلۡأٓيَٰتِ لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ٢٧
فَلَوۡلَا نَصَرَهُمُ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ قُرۡبَانًا ءَالِهَةَۖ
بَلۡ ضَلُّواْ عَنۡهُمۡۚ وَذَٰلِكَ إِفۡكُهُمۡ وَمَا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ ٢٨

(21) Ka kuma tuna ɗan'uwan Adawa (watau Hudu) lokacin da ya gargaɗi mutanensa a al-Ahkafu, alhali hakika masu gargaɗi sun shuɗe a gabaninsa da kuma a bayansa (suna cewa:) "Kada ku bauta wa (kowa) sai Allah, lalle ni ina jiye muku tsoron azabar wani yini mai girma."

(22) Sai suka ce: "Yanzu ka zo ne don ka kawar da mu daga ababen bautarmu? To ka zo mana da abin da kake yi mana alkawarin narko (da shi) idan ka kasance cikin masu gaskiya."

(23) Sai ya ce: "Lalle sani yana wurin Allah kawai, ni kuma ina isar muku abin da aka aiko ni da shi ne, sai dai kuma ni ina ganin ku mutane ne masu wauta."

(24) To lokacin da suka gan ta (azabar) wani hadari ne mai gindayawa, ya doso wa kwarurukansu sai suka ce: "Wannan hadari ne mai ba mu ruwa!" A'a, (ba ku sani ba) shi ne abin da kuke neman gaggautowarsa, watau iska da take cike da azaba mai raɗaɗi

(25) Tana ruguza kowane irin abu da umarnin Ubangijinta, sai suka wayi gari ba abin da ake gani sai (kufaifan) gidajensu. Kamar haka Muke saka wa mutane masu manyan laifuka

(26) Hakika Mun kafa su (a bayan ƙasa) kafawar da ba Mu yi muku irinta ba, Muka kuma sanya musu ji da gani da tunani, sai jin nasu da ganinsu da tunaninsu ba su amfana musu komai ba, tunda sun kasance suna musanta ayoyin Allah, abin da kuma suka kasance suna yi wa izgili ya auka musu

(27) Hakika mun hallakar da abin da yake kewaye da ku na (mutanen) alkaryu[1], Mun kuma jujjuya musu ayoyi (ta fuskoki daban-daban) don su dawo (kan hanya)

(28) To me ya hana allolin da suka riƙe suna bautar su ba Allah ba, su taimake su? A'a, sun dai ɓace musu ne. Wannan kuma da man ƙaryarsu ce da kuma abin da suka kasance suna ƙagawa

(1) Watau kafirai da suka yi maqotaka da su, kamar Adawa da Samudawa da mutanen Annabi Lux ( ) da mutanen Madyana.

وَإِذْ صَرَفْنَآ إِلَيْكَ نَفَرًا مِّنَ ٱلْجِنِّ يَسْتَمِعُونَ ٱلْقُرْءَانَ فَلَمَّا
حَضَرُوهُ قَالُوٓا۟ أَنصِتُوا۟ ۖ فَلَمَّا قُضِىَ وَلَّوْا۟ إِلَىٰ قَوْمِهِم مُّنذِرِينَ
﴿٢٩﴾ قَالُوا۟ يَٰقَوْمَنَآ إِنَّا سَمِعْنَا كِتَٰبًا أُنزِلَ مِنۢ بَعْدِ مُوسَىٰ
مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ يَهْدِىٓ إِلَى ٱلْحَقِّ وَإِلَىٰ طَرِيقٍ مُّسْتَقِيمٍ
﴿٣٠﴾ يَٰقَوْمَنَآ أَجِيبُوا۟ دَاعِىَ ٱللَّهِ وَءَامِنُوا۟ بِهِۦ يَغْفِرْ لَكُم مِّن
ذُنُوبِكُمْ وَيُجِرْكُم مِّنْ عَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿٣١﴾ وَمَن لَّا يُجِبْ دَاعِىَ ٱللَّهِ
فَلَيْسَ بِمُعْجِزٍ فِى ٱلْأَرْضِ وَلَيْسَ لَهُۥ مِن دُونِهِۦٓ أَوْلِيَآءُ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ
فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٣٢﴾ أَوَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّ ٱللَّهَ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضَ وَلَمْ يَعْىَ بِخَلْقِهِنَّ بِقَٰدِرٍ عَلَىٰٓ أَن يُحْۦِىَ ٱلْمَوْتَىٰ ۚ بَلَىٰٓ
إِنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٣٣﴾ وَيَوْمَ يُعْرَضُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ عَلَى ٱلنَّارِ
أَلَيْسَ هَٰذَا بِٱلْحَقِّ ۖ قَالُوا۟ بَلَىٰ وَرَبِّنَا ۚ قَالَ فَذُوقُوا۟ ٱلْعَذَابَ بِمَا
كُنتُمْ تَكْفُرُونَ ﴿٣٤﴾ فَٱصْبِرْ كَمَا صَبَرَ أُو۟لُوا۟ ٱلْعَزْمِ مِنَ ٱلرُّسُلِ
وَلَا تَسْتَعْجِل لَّهُمْ ۚ كَأَنَّهُمْ يَوْمَ يَرَوْنَ مَا يُوعَدُونَ لَمْ يَلْبَثُوٓا۟ إِلَّا
سَاعَةً مِّن نَّهَارٍ ۚ بَلَٰغٌ ۚ فَهَلْ يُهْلَكُ إِلَّا ٱلْقَوْمُ ٱلْفَٰسِقُونَ ﴿٣٥﴾

سُورَةُ مُحَمَّدٍ

(29) (Ka tuna) kuma lokacin da Muka juyo maka da wata jama'a ta aljannu don su saurari Alkur'ani(1). To lokacin da suka halarto shi, sai suka ce: "Ku yi shiru;" sannan lokacin da aka gama (karatunsa) sai suka juya zuwa mutanensu suna yi musu gargadi

(30) Suka ce: "Ya ku mutanenmu, hakika mu mun jiwo wani littafi da aka saukar bayan Musa, mai gaskata abin da yake gabaninsa, yana shiryarwa zuwa gaskiya da kuma zuwa tafarki madaidaici

(31) "Ya ku mutanenmu, ku amsa wa mai kira (zuwa ga) Allah(7), kuma ku yi imani da shi, (Allah) zai gafarta muku zunubanku ya kuma tsare ku daga azaba mai radadi

(32) "Duk wanda kuwa bai amsa wa mai kira (zuwa ga) Allah ba, to ba zai gagara ba a bayan kasa, kuma ba shi da wasu mataimaka in ba shi ba. Wadannan suna cikin bata mabayyani

(33) Ba sa ganin cewa Allah wanda Ya halicci sammai da kasa, Bai kuma gajiya ba wajen halittar su, Mai iko ne kan Ya raya matattu? Haka ne, lalle Shi Mai iko ne a kan komai

(34) Kuma a ranar da za a bijiro da wadanda suka kafirta a gaban wuta (a ce da su): "Yanzu wannan ba gaskiya ba ne?" Suka ce: "Haka ne (gaskiya ne) Mun rantse da Ubangijinmu." Sai Ya ce: "To ku dandani azaba saboda abin da kuka kasance kuna yi na kafirci."

(35) To ka yi hakuri kamar yadda masu azama daga manzanni suka yi hakuri, kada kuma ka nemi gaggauto musu (azaba). Kai ka ce ranar da za su ga abin da ake yi musu alkawarinsa kamar ba su zauna (a duniya) ba sai wani dan lokaci na wuni. (Wannan) isar da sako ne. To akwai wadanda za a halakar in ba mutane fasikai ba?

(1) Su ne wasu aljannu da suka saurari karatun Annabi ( ) a wani wuri da ake kira Baxnu Nakhla, lokacin da yake yi wa sahabbansa sallar asuba.

(2) Watau Annabi Muhammad ( ).

Sura Muhammad

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَصَدُّوا۟ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ أَضَلَّ أَعْمَٰلَهُمْ ﴿١﴾ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَءَامَنُوا۟ بِمَا نُزِّلَ عَلَىٰ مُحَمَّدٍ وَهُوَ ٱلْحَقُّ مِن
رَّبِّهِمْ كَفَّرَ عَنْهُمْ سَيِّـَٔاتِهِمْ وَأَصْلَحَ بَالَهُمْ ﴿٢﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟
ٱتَّبَعُوا۟ ٱلْبَٰطِلَ وَأَنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱتَّبَعُوا۟ ٱلْحَقَّ مِن رَّبِّهِمْ ۚ كَذَٰلِكَ يَضْرِبُ
ٱللَّهُ لِلنَّاسِ أَمْثَٰلَهُمْ ﴿٣﴾ فَإِذَا لَقِيتُمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ فَضَرْبَ ٱلرِّقَابِ حَتَّىٰٓ
إِذَآ أَثْخَنتُمُوهُمْ فَشُدُّوا۟ ٱلْوَثَاقَ فَإِمَّا مَنًّۢا بَعْدُ وَإِمَّا فِدَآءً حَتَّىٰ تَضَعَ ٱلْحَرْبُ
أَوْزَارَهَا ۚ ذَٰلِكَ ۖ وَلَوْ يَشَآءُ ٱللَّهُ لَٱنتَصَرَ مِنْهُمْ وَلَٰكِن لِّيَبْلُوَا۟ بَعْضَكُم
بِبَعْضٍ ۗ وَٱلَّذِينَ قُتِلُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ فَلَن يُضِلَّ أَعْمَٰلَهُمْ ﴿٤﴾ سَيَهْدِيهِمْ
وَيُصْلِحُ بَالَهُمْ ﴿٥﴾ وَيُدْخِلُهُمُ ٱلْجَنَّةَ عَرَّفَهَا لَهُمْ ﴿٦﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوٓا۟ إِن تَنصُرُوا۟ ٱللَّهَ يَنصُرْكُمْ وَيُثَبِّتْ أَقْدَامَكُمْ ﴿٧﴾ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟
فَتَعْسًا لَّهُمْ وَأَضَلَّ أَعْمَٰلَهُمْ ﴿٨﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ كَرِهُوا۟ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ
فَأَحْبَطَ أَعْمَٰلَهُمْ ﴿٩﴾ ۞ أَفَلَمْ يَسِيرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ فَيَنظُرُوا۟ كَيْفَ كَانَ
عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ ۖ دَمَّرَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمْ ۖ وَلِلْكَٰفِرِينَ أَمْثَٰلُهَا ﴿١٠﴾ ذَٰلِكَ
بِأَنَّ ٱللَّهَ مَوْلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَأَنَّ ٱلْكَٰفِرِينَ لَا مَوْلَىٰ لَهُمْ ﴿١١﴾

(1) Wadanda suka kafirta suka kuma toshe hanyar Allah, to (Allah) Ya lalata ayyukansu[1]
(2) Wadanda kuwa suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, kuma suka gaskata abin da aka saukar wa Muhammadu alhali kuwa shi ne gaskiya daga Ubangijinsu, sai (Allah) Ya kankare musu munanan ayyukansu, Ya kuma gyara musu halayensu
(3) Wadanda kuwa suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, kuma suka gaskata abin da aka saukar wa Muhammadu alhali kuwa shi ne gaskiya daga Ubangijinsu, sai (Allah) Ya kankare musu munanan ayyukansu, Ya kuma gyara musu halayensu (4) To idan kuka hadu da wadanda suka kafirta sai ku sare wuyoyinsu har lokacin da kuka yi musu jina-jina, sai ku tsananta dauri[2]; to bayan nan ko dai yafewa su tafi bayan (kun ribace su), ko kuma karbar fansa har sai yaki ya lafa. Wannan abu haka yake, da kuma Allah Ya ga dama da Ya yi nasara a kansu (ko da ba yaki), sai dai kuma (Ya yi haka ne) don Ya jarrabi shashinku da shashi. Wadanda kuwa aka kashe su a hanyar Allah, to ba zai taba lalata ayyukansa ba (5) Zai shirye su Ya kuma kyautata halinsu (6) Ya kuma shigar da su Aljannar da Ya sanar da ita gare su (7) Ya ku wadanda suka yi imani idan kuka taimaki Allah, to zai taimake ku, Ya kuma tabbatar da dugaduganku
(8) Wadanda kuwa suka kafirce to kaiconsu, (Allah) kuma Ya lalata ayyukansu[3] (9) Wannan kuwa saboda cewa sun ki abin da Allah Ya saukar, sai Ya lalata ayyukansu (10)Yanzu ba za su yi tafiya a bayan kasa ba sai su duba yaya karshen wadanda suka gabace su ya kasance? Allah Ya hallaka su; kafirai kuma suna da (sakamako) kwatankwacinsa. (11) Wannan kuwa saboda lalle Allah ne Majibincin al'amuran wadanda suka yi imani, lalle kuma su kafirai ba su da wani majibinci

(1) Watau ba za su sami lada ba a kan ayyuka na qwarai da suka yi. Hakanan ayyukansu da suke yi na qoqarin rushe Musulunci haqansu ba zai cimma ruwa ba.

(2) Watau Musulmi su kama su a matsayin ribatattun yaqi.

(3) Watau ba za su sami ladan wani aiki nasu na qwarai ba, kuma ayyukansu na qoqarin rushe Musulunci ba za su yi nasara ba.

إِنَّ ٱللَّهَ يُدۡخِلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن
تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يَتَمَتَّعُونَ وَيَأۡكُلُونَ كَمَا تَأۡكُلُ ٱلۡأَنۡعَٰمُ
وَٱلنَّارُ مَثۡوٗى لَّهُمۡ ١٢ وَكَأَيِّن مِّن قَرۡيَةٍ هِيَ أَشَدُّ قُوَّةٗ مِّن قَرۡيَتِكَ
ٱلَّتِيٓ أَخۡرَجَتۡكَ أَهۡلَكۡنَٰهُمۡ فَلَا نَاصِرَ لَهُمۡ ١٣ أَفَمَن كَانَ عَلَىٰ بَيِّنَةٖ مِّن
رَّبِّهِۦ كَمَن زُيِّنَ لَهُۥ سُوٓءُ عَمَلِهِۦ وَٱتَّبَعُوٓاْ أَهۡوَآءَهُمۡ ١٤ مَّثَلُ ٱلۡجَنَّةِ ٱلَّتِي
وُعِدَ ٱلۡمُتَّقُونَۖ فِيهَآ أَنۡهَٰرٞ مِّن مَّآءٍ غَيۡرِ ءَاسِنٖ وَأَنۡهَٰرٞ مِّن لَّبَنٖ لَّمۡ يَتَغَيَّرۡ
طَعۡمُهُۥ وَأَنۡهَٰرٞ مِّنۡ خَمۡرٖ لَّذَّةٖ لِّلشَّٰرِبِينَ وَأَنۡهَٰرٞ مِّنۡ عَسَلٖ مُّصَفّٗىۖ وَلَهُمۡ
فِيهَا مِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ وَمَغۡفِرَةٞ مِّن رَّبِّهِمۡۖ كَمَنۡ هُوَ خَٰلِدٞ فِي ٱلنَّارِ وَسُقُواْ
مَآءً حَمِيمٗا فَقَطَّعَ أَمۡعَآءَهُمۡ ١٥ وَمِنۡهُم مَّن يَسۡتَمِعُ إِلَيۡكَ حَتَّىٰٓ إِذَا
خَرَجُواْ مِنۡ عِندِكَ قَالُواْ لِلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ مَاذَا قَالَ ءَانِفًاۚ أُوْلَٰٓئِكَ
ٱلَّذِينَ طَبَعَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ وَٱتَّبَعُوٓاْ أَهۡوَآءَهُمۡ ١٦ وَٱلَّذِينَ ٱهۡتَدَواْ
زَادَهُمۡ هُدٗى وَءَاتَىٰهُمۡ تَقۡوَىٰهُمۡ ١٧ فَهَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّا ٱلسَّاعَةَ
أَن تَأۡتِيَهُم بَغۡتَةٗۖ فَقَدۡ جَآءَ أَشۡرَاطُهَاۚ فَأَنَّىٰ لَهُمۡ إِذَا جَآءَتۡهُمۡ
ذِكۡرَىٰهُمۡ ١٨ فَٱعۡلَمۡ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لِذَنۢبِكَ
وَلِلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِۗ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مُتَقَلَّبَكُمۡ وَمَثۡوَىٰكُمۡ ١٩

(12) Lalle Allah Yana shigar da waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari gidajen Aljanna (waɗanda) ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu; waɗanda kuwa suka kafirta suna jin dadi (a duniya), suna kuma ta ciye-ciye kamar yadda dabbobi suke yi, wuta ce kuma makomarsu

(13) Alƙaryu nawa ne waɗanda suka fi alƙaryarka wadda ta fitar da kai ƙarfi, Mun hallakar da su, don haka ba su da wani mai taimakon su

(14) Yanzu waɗanda suka kasance a kan hujja daga Ubangijinsu, sa yi daidai da waɗanda aka ƙawata musu mummuna aikinsu, suka kuma bi son zuciyarsu? (15) Kwatankwacin Aljannar da aka yi wa masu taƙawa alƙawari da ita shi ne, a cikinta akwai ƙoramu na ruwa ba gurɓatacce ba, da kuma ƙoramu na nono da ɗanɗanonsa bai canja ba, da ƙoramu na giya masu daɗi ga mashaya, da ƙoramu na tatacciyar zuma, kuma suna da kowane irin nau'i na 'ya'yan itace da kuma gafara daga Ubangijinsu. Yanzu (masu waɗannan sa yi) daidai da waɗanda za su dawwama a cikin wuta a kuma shayar da su ruwa tafasasshe, sai ya yayyanke kayan cikinsu? (16) Daga cikinsu kuma akwai waɗanda suke sauraron ka, har lokacin da suka fita daga wurinka sai su ce da waɗanda aka bai wa ilimi: "Shin me ma ya ce ɗazu?" Waɗannan su ne waɗanda Allah Ya toshe zukatansu suka kuma bi son ransu(17) Waɗanda kuwa suka shiryu Ya ƙara musu shiriya, Ya kuma kimsa musu taƙawarsu(18) Ai ba wani abu da suke sauraro sai alƙiyama ta zo musu farat ɗaya; to haƙiƙa alamominta sun zo[1] . To ƙaƙa tunawar tasu za ta zame musu idan abin (alƙiyamar) ta zo musu ne? (19) To ka sani cewa, babu wani abin bauta da gaskiya sai Allah, kuma ka nemi gafarar zunubanka da na muminai maza da mata, Allah kuma Yana sane da kai-kawonku (na rana) da kuma wurin kwanciyarku (da daddare)

(1) Daga cikinsu akwai aiko da Manzon Allah ( ) da tsagewar wata gida biyu da ya faru a Makka.

وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَوْلَا نُزِّلَتْ سُورَةٌ ۖ فَإِذَآ أُنزِلَتْ سُورَةٌ
مُّحْكَمَةٌ وَذُكِرَ فِيهَا ٱلْقِتَالُ رَأَيْتَ ٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ
يَنظُرُونَ إِلَيْكَ نَظَرَ ٱلْمَغْشِىِّ عَلَيْهِ مِنَ ٱلْمَوْتِ ۖ فَأَوْلَىٰ لَهُمْ
﴿٢٠﴾ طَاعَةٌ وَقَوْلٌ مَّعْرُوفٌ ۚ فَإِذَا عَزَمَ ٱلْأَمْرُ فَلَوْ صَدَقُوا۟ ٱللَّهَ
لَكَانَ خَيْرًا لَّهُمْ ﴿٢١﴾ فَهَلْ عَسَيْتُمْ إِن تَوَلَّيْتُمْ أَن تُفْسِدُوا۟
فِى ٱلْأَرْضِ وَتُقَطِّعُوٓا۟ أَرْحَامَكُمْ ﴿٢٢﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَعَنَهُمُ
ٱللَّهُ فَأَصَمَّهُمْ وَأَعْمَىٰٓ أَبْصَٰرَهُمْ ﴿٢٣﴾ أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ ٱلْقُرْءَانَ
أَمْ عَلَىٰ قُلُوبٍ أَقْفَالُهَآ ﴿٢٤﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱرْتَدُّوا۟ عَلَىٰٓ أَدْبَٰرِهِم
مِّنۢ بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلْهُدَى ٱلشَّيْطَٰنُ سَوَّلَ لَهُمْ وَأَمْلَىٰ
لَهُمْ ﴿٢٥﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَالُوا۟ لِلَّذِينَ كَرِهُوا۟ مَا نَزَّلَ ٱللَّهُ
سَنُطِيعُكُمْ فِى بَعْضِ ٱلْأَمْرِ ۖ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ إِسْرَارَهُمْ ﴿٢٦﴾
فَكَيْفَ إِذَا تَوَفَّتْهُمُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَضْرِبُونَ وُجُوهَهُمْ
وَأَدْبَٰرَهُمْ ﴿٢٧﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمُ ٱتَّبَعُوا۟ مَآ أَسْخَطَ ٱللَّهَ
وَكَرِهُوا۟ رِضْوَٰنَهُۥ فَأَحْبَطَ أَعْمَٰلَهُمْ ﴿٢٨﴾ أَمْ حَسِبَ
ٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ أَن لَّن يُخْرِجَ ٱللَّهُ أَضْغَٰنَهُمْ ﴿٢٩﴾

(20) Waɗanda kuma suka yi imani suna cewa: “Me ya hana a saukar da wata sura (wadda za ta ba mu damar yin yaƙi)?” Sannan lokacin da aka saukar da wata sura mai ɗauke da hukunci aka kuma ambaci yaƙi a cikinta, sai ka ga waɗanda suke da raunin imani a zukatansu (watau munafukai), suna kallon ka kamar kallon wanda yake cikin magagin mutuwa. To abin da ya fiye musu
(21) (Shi ne) yin biyayya da magana mai kyau. To idan al’amarin yaƙi ya tabbata, to da za su nuna wa Allah gaskiyarsu, da ya fi musu alhairi
(22)Shin ba kwa ganin idan kuka ba da baya (daga bin Allah) sai ku yi ɓarna a bayan ƙasa, ku kuma yanke zumuntarku?
(23) Waɗannan su ne waɗanda Allah Ya la’ance su, sai Ya kurumtar da su, Ya kuma makantar da ganinsu
(24) Yanzu ba za su yi tunani na basira ba (game da) Alƙur’ani ba, ko kuwa akwai wani rufi ne a kan zukatansu?
(25) Lalle waɗanda suka yi ridda suka koma baya, bayan kuwa shiriya ta bayyana a gare su, to Shaiɗan ne ya ƙawata musu ya kuma yi musu shifta
(26) Wannan kuwa saboda lalle su, sun ce wa waɗanda suka ƙi bin abin da Allah Ya saukar: “Za mu bi ku a wasu al’amura.” Allah kuwa Yana sane da asiransu
(27) To yaya za su zama lokacin da mala’iku za su karɓi rayukansu suna dukan fuskokinsu da bayansu?
(28) Wannan kuwa saboda lalle su, sun bi abin da yake fusata Allah suka kuma ƙi bin yardarsa, sai ya rusa ayyukansa
(29) Ko kuwa waɗanda suke da cuta a cikin zukatansu suna tsammanin cewa Allah ba zai fito da ƙulle-ƙullen zukatansu ba ne?

وَلَوْ نَشَآءُ لَأَرَيْنَٰكَهُمْ فَلَعَرَفْتَهُم بِسِيمَٰهُمْ ۚ وَلَتَعْرِفَنَّهُمْ فِى
لَحْنِ ٱلْقَوْلِ ۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ أَعْمَٰلَكُمْ ﴿٣٠﴾ وَلَنَبْلُوَنَّكُمْ حَتَّىٰ نَعْلَمَ
ٱلْمُجَٰهِدِينَ مِنكُمْ وَٱلصَّٰبِرِينَ وَنَبْلُوَا۟ أَخْبَارَكُمْ ﴿٣١﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ وَصَدُّوا۟ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَشَآقُّوا۟ ٱلرَّسُولَ مِنۢ بَعْدِ
مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلْهُدَىٰ لَن يَضُرُّوا۟ ٱللَّهَ شَيْـًٔا ۗ وَسَيُحْبِطُ أَعْمَٰلَهُمْ
﴿٣٢﴾ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَطِيعُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُوا۟ ٱلرَّسُولَ
وَلَا تُبْطِلُوٓا۟ أَعْمَٰلَكُمْ ﴿٣٣﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَصَدُّوا۟ عَن سَبِيلِ
ٱللَّهِ ثُمَّ مَاتُوا۟ وَهُمْ كُفَّارٌ فَلَن يَغْفِرَ ٱللَّهُ لَهُمْ ﴿٣٤﴾ فَلَا تَهِنُوا۟
وَتَدْعُوٓا۟ إِلَى ٱلسَّلْمِ وَأَنتُمُ ٱلْأَعْلَوْنَ وَٱللَّهُ مَعَكُمْ وَلَن يَتِرَكُمْ
أَعْمَٰلَكُمْ ﴿٣٥﴾ إِنَّمَا ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا لَعِبٌ وَلَهْوٌ ۚ وَإِن تُؤْمِنُوا۟ وَتَتَّقُوا۟
يُؤْتِكُمْ أُجُورَكُمْ وَلَا يَسْـَٔلْكُمْ أَمْوَٰلَكُمْ ﴿٣٦﴾ إِن يَسْـَٔلْكُمُوهَا
فَيُحْفِكُمْ تَبْخَلُوا۟ وَيُخْرِجْ أَضْغَٰنَكُمْ ﴿٣٧﴾ هَٰٓأَنتُمْ هَٰٓؤُلَآءِ
تُدْعَوْنَ لِتُنفِقُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۖ فَمِنكُم مَّن يَبْخَلُ ۖ وَمَن يَبْخَلْ
فَإِنَّمَا يَبْخَلُ عَن نَّفْسِهِۦ ۚ وَٱللَّهُ ٱلْغَنِىُّ وَأَنتُمُ ٱلْفُقَرَآءُ ۚ وَإِن
تَتَوَلَّوْا۟ يَسْتَبْدِلْ قَوْمًا غَيْرَكُمْ ثُمَّ لَا يَكُونُوٓا۟ أَمْثَٰلَكُم ﴿٣٨﴾

(30) Kuma da Mun ga dama da tabbas Mun nuna maka su (watau munafukai), to tabbas da ka gane su da alamominsu. Kuma tabbas za ka iya gane su ta hanyar salon maganarsu. Allah kuma Yana sane da ayyukanku

(31) Kuma tabbas za Mu jarraba ku har sai Mun bayyana masu jihadi daga cikinku, da masu haƙuri, kuma za Mu bayyana halayenku

(32) Lalle waɗanda suka kafirta suka kuma toshe hanyar Allah, kuma suka saɓa wa Manzo bayan shiriya ta bayyana a gare su, to ba za su taɓa cutar Allah da komai ba, kuma zai lalata ayyukansu

(33) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku bi Allah, kuma ku bi Manzonsa, kada kuma ku ɓata ayyukanku[1]

(34) Lalle waɗanda suka kafirta suka kuma toshe hanyar Allah, sannan suka mutu a halin suna kafirai, to Allah ba zai taɓa gafarta musu ba

(35) To kada ku raunana, kuma kada ku kirawo su zuwa sulhu[2], alhali ku ne a sama, Allah kuwa Yana tare da ku, kuma ba zai tauye muku ayyukanku ba

(36) Rayuwar duniya wasa ce da sharholiya kawai. Idan kuwa kuka yi imani kuka kiyaye dokokin Allah, to zai ba ku ladanku, ba kuma zai tambaye ku ku ba da dukiyoyinku (duka) ba

(37) Don ko idan da zai tambaye ku ita (dukiyar gaba ɗaya) Ya kuma nace muku, to da sai ku yi rowa, Ya kuma fito da ƙulle-ƙullen zukatanku

(38) To ga ku fa ku ɗin nan ana kiran ku don ku ciyar a hanyar Allah, to daga cikinku akwai masu yin rowa; wanda kuwa duk ya yi rowa, lalle ya yi wa kansa rowa ne. Allah kuma Mawadaci ne, ku ne mabuƙata. Idan kuwa kuka ba da baya to zai canja wasu mutanen ba ku ba, sannan ba za su zama kamar ku ba

(1) Watau ta hanyar aikata kafirci ko munafurci ko riya.

(2) Watau gabanin su kafiran su nuna suna son sulhu.

Sura Fat'h

سُورَةُ الفَتۡحِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِنَّا فَتَحۡنَا لَكَ فَتۡحٗا مُّبِينٗا ١ لِّيَغۡفِرَ لَكَ ٱللَّهُ مَا تَقَدَّمَ مِن ذَنۢبِكَ
وَمَا تَأَخَّرَ وَيُتِمَّ نِعۡمَتَهُۥ عَلَيۡكَ وَيَهۡدِيَكَ صِرَٰطٗا مُّسۡتَقِيمٗا ٢
وَيَنصُرَكَ ٱللَّهُ نَصۡرًا عَزِيزًا ٣ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ ٱلسَّكِينَةَ فِي قُلُوبِ
ٱلۡمُؤۡمِنِينَ لِيَزۡدَادُوٓاْ إِيمَٰنٗا مَّعَ إِيمَٰنِهِمۡۗ وَلِلَّهِ جُنُودُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمٗا ٤ لِّيُدۡخِلَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ
جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَيُكَفِّرَ عَنۡهُمۡ
سَيِّـَٔاتِهِمۡۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عِندَ ٱللَّهِ فَوۡزًا عَظِيمٗا ٥ وَيُعَذِّبَ
ٱلۡمُنَٰفِقِينَ وَٱلۡمُنَٰفِقَٰتِ وَٱلۡمُشۡرِكِينَ وَٱلۡمُشۡرِكَٰتِ ٱلظَّآنِّينَ
بِٱللَّهِ ظَنَّ ٱلسَّوۡءِۚ عَلَيۡهِمۡ دَآئِرَةُ ٱلسَّوۡءِۖ وَغَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡ
وَلَعَنَهُمۡ وَأَعَدَّ لَهُمۡ جَهَنَّمَۖ وَسَآءَتۡ مَصِيرٗا ٦ وَلِلَّهِ جُنُودُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا ٧ إِنَّآ
أَرۡسَلۡنَٰكَ شَٰهِدٗا وَمُبَشِّرٗا وَنَذِيرٗا ٨ لِّتُؤۡمِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ
وَتُعَزِّرُوهُ وَتُوَقِّرُوهُ وَتُسَبِّحُوهُ بُكۡرَةٗ وَأَصِيلًا ٩

(1) Lalle Mu ne Muka yi maka budi, budi mabayyani[1]
(2) Don Allah Ya gafarta maka abin da ya gabata na zunubinka, da kuma wanda ya jinkirta, Ya kuma cika maka ni'imarsa, kuma Ya shiryar da kai hanya madaidaiciya
(3) Allah kuma zai taimake ka da nasara mai girma
(4) Shi ne wanda Ya sanya nutsuwa a zukatan muminai[2]don su ƙara imani a kan imaninsu. Rundunonin sammai da ƙasa kuma na Allah ne, kuma Allah Ya kasance Masani ne, Mai hikima
(5) (Ya yi haka ne) don Ya shigar da muminai maza da mata gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu suna masu dawwama a cikinsu, Ya kuma kankare musu laifukansu. Wannan kuwa ya kasance babban rabo ne a wurin Allah
(6) Ya kuma azabtar da munafukai maza da mata, da mushirikai maza da mata, masu munana zato ga Allah. Mummunar azaba ta koma a kansu; kuma Allah Ya yi fushi da su, Ya kuma la'ance su, Ya kuma tanadar musu Jahannama; makoma kuwa ta munana
(7) Kuma rundunonin sammai da ƙasa na Allah ne. Allah kuwa Ya kasance Mabuwayi ne, Mai hikima
(8) Lalle Mu Muka aiko ka don ka zama sheda kuma mai albishir mai gargaɗi
(9) Don (ku mutane) ku yi imani da Allah da Manzonsa ku kuma taimake shi (wato Annabinsa), kuma ku girmama shi, ku kuma tsarkake Shi (wato Allah) safe da yamma

(1) Watau ya ba shi nasara ta hanyar sulhun Hudaibiyya, wata yarjejeniya da Musulmi suka qulla da Quraishawa a shekara ta shida, don tsagaita yaqi a tsakaninsu har tsawon shekara goma.

(2) Watau bayan muminai suna ganin sharuxxan sulhun ba su yi musu daxi ba, amma Allah ya saukar musu da nutsuwa a cikin zukatansu.

إِنَّ ٱلَّذِينَ يُبَايِعُونَكَ إِنَّمَا يُبَايِعُونَ ٱللَّهَ يَدُ ٱللَّهِ فَوْقَ
أَيْدِيهِمْ ۚ فَمَن نَّكَثَ فَإِنَّمَا يَنكُثُ عَلَىٰ نَفْسِهِۦ ۖ وَمَنْ أَوْفَىٰ
بِمَا عَٰهَدَ عَلَيْهُ ٱللَّهَ فَسَيُؤْتِيهِ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿١٠﴾ سَيَقُولُ
لَكَ ٱلْمُخَلَّفُونَ مِنَ ٱلْأَعْرَابِ شَغَلَتْنَآ أَمْوَٰلُنَا وَأَهْلُونَا
فَٱسْتَغْفِرْ لَنَا ۚ يَقُولُونَ بِأَلْسِنَتِهِم مَّا لَيْسَ فِى قُلُوبِهِمْ ۚ قُلْ
فَمَن يَمْلِكُ لَكُم مِّنَ ٱللَّهِ شَيْـًٔا إِنْ أَرَادَ بِكُمْ ضَرًّا أَوْ أَرَادَ بِكُمْ
نَفْعًا ۚ بَلْ كَانَ ٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرًا ﴿١١﴾ بَلْ ظَنَنتُمْ أَن لَّن
يَنقَلِبَ ٱلرَّسُولُ وَٱلْمُؤْمِنُونَ إِلَىٰٓ أَهْلِيهِمْ أَبَدًا وَزُيِّنَ ذَٰلِكَ فِى
قُلُوبِكُمْ وَظَنَنتُمْ ظَنَّ ٱلسَّوْءِ وَكُنتُمْ قَوْمًۢا بُورًا ﴿١٢﴾ وَمَن لَّمْ يُؤْمِنۢ
بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ فَإِنَّآ أَعْتَدْنَا لِلْكَٰفِرِينَ سَعِيرًا ﴿١٣﴾ وَلِلَّهِ مُلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ يَغْفِرُ لِمَن يَشَآءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ ۚ
وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿١٤﴾ سَيَقُولُ ٱلْمُخَلَّفُونَ إِذَا
ٱنطَلَقْتُمْ إِلَىٰ مَغَانِمَ لِتَأْخُذُوهَا ذَرُونَا نَتَّبِعْكُمْ ۖ يُرِيدُونَ
أَن يُبَدِّلُوا۟ كَلَٰمَ ٱللَّهِ ۚ قُل لَّن تَتَّبِعُونَا كَذَٰلِكُمْ قَالَ ٱللَّهُ مِن قَبْلُ ۖ
فَسَيَقُولُونَ بَلْ تَحْسُدُونَنَا ۚ بَلْ كَانُوا۟ لَا يَفْقَهُونَ إِلَّا قَلِيلًا ﴿١٥﴾

(10) Lalle wadanda suka yi maka mubaya'a[1] Allah kawai suke yi wa mubaya'a, Hannun Allah yana saman hannayensu. To duk wanda ya warware, to kansa kawai ya warware wa, wanda kuwa ya cika abin da ya yi wa Allah alkawarinsa, to ba da dadewa ba za Mu ba shi lada mai girma

(11) Wadanda suka ki fita da kai daga cikin mutanen kauye za su ce maka: "Dukiyoyinmu da iyalinmu ne suka shagaltar da mu, sai ka nema mana gafara." Da harsunansu suna fadar abin da ba ya cikin zukatansu. Ka ce: "To wa zai amfana muku wani abu ne a wajen Allah idan Ya yi nufin ku da cutuwa, ko kuma Ya yi nufin ku da alhairi?" A'a, Allah yana sane da abin da kuka kasance kuna aikatawa

(12) "A'a, ku dai kun zaci cewa Manzo da muminai ba za su komo wajen iyalinsu ba har abada, aka kuma kawata wannan a cikin zukatanku, kuka kuma yi mummunan zato, kuma kun kasance mutane halakakku."

(13) Duk kuwa wanda bai yi imani da Allah da Manzonsa ba, to lalle Mu Mun tanadi wutar Sa'ira ga kafirai

(14) Kuma mulkin sammai da kasa na Allah ne. Yana yin gafara ga wanda Ya ga dama, Yana kuma azabtar da wanda Ya ga dama. Allah kuwa Ya kasance Mai gafara ne, Mai rahama

(15) Wadanda suka ki fita tare da kai[2] za su ce, lokacin da kuka tafi zuwa wasu wuraren ganima don ku samo ta: "Ku bar mu mu bi ku"[3], suna nufin su musanya zancen Allah ne. Ka ce: "Ba za ku bi mu ba, da ma tuni haka Allah Ya fada." To za su ce: "A'a, kuna yi mana hassada ne kawai." Ba haka ba ne, sun kasance ba sa fahimta ne sai 'yan kadan

(1) Su ne sahabbai dubu da xari huxu da suka yi wa Annabi ( ) mubaya'ar yaqi a Hudaibiyya, watau Bai'atur Ridhwan.

(2) Watau suka fita tare da Annabi ( ) zuwa Makka.

(3) Watau zuwa Khaibar.

قُل لِّلْمُخَلَّفِينَ مِنَ ٱلْأَعْرَابِ سَتُدْعَوْنَ إِلَىٰ قَوْمٍ أُو۟لِى بَأْسٍ شَدِيدٍ
تُقَٰتِلُونَهُمْ أَوْ يُسْلِمُونَ ۖ فَإِن تُطِيعُوا۟ يُؤْتِكُمُ ٱللَّهُ أَجْرًا حَسَنًا ۖ
وَإِن تَتَوَلَّوْا۟ كَمَا تَوَلَّيْتُم مِّن قَبْلُ يُعَذِّبْكُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿١٦﴾ لَّيْسَ
عَلَى ٱلْأَعْمَىٰ حَرَجٌ وَلَا عَلَى ٱلْأَعْرَجِ حَرَجٌ وَلَا عَلَى ٱلْمَرِيضِ حَرَجٌ ۗ
وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ يُدْخِلْهُ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا
ٱلْأَنْهَٰرُ ۖ وَمَن يَتَوَلَّ يُعَذِّبْهُ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿١٧﴾ ۞ لَّقَدْ رَضِىَ ٱللَّهُ
عَنِ ٱلْمُؤْمِنِينَ إِذْ يُبَايِعُونَكَ تَحْتَ ٱلشَّجَرَةِ فَعَلِمَ مَا فِى
قُلُوبِهِمْ فَأَنزَلَ ٱلسَّكِينَةَ عَلَيْهِمْ وَأَثَٰبَهُمْ فَتْحًا قَرِيبًا ﴿١٨﴾ وَمَغَانِمَ
كَثِيرَةً يَأْخُذُونَهَا ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا ﴿١٩﴾ وَعَدَكُمُ ٱللَّهُ
مَغَانِمَ كَثِيرَةً تَأْخُذُونَهَا فَعَجَّلَ لَكُمْ هَٰذِهِۦ وَكَفَّ أَيْدِىَ
ٱلنَّاسِ عَنكُمْ وَلِتَكُونَ ءَايَةً لِّلْمُؤْمِنِينَ وَيَهْدِيَكُمْ صِرَٰطًا
مُّسْتَقِيمًا ﴿٢٠﴾ وَأُخْرَىٰ لَمْ تَقْدِرُوا۟ عَلَيْهَا قَدْ أَحَاطَ ٱللَّهُ بِهَا ۚ
وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرًا ﴿٢١﴾ وَلَوْ قَٰتَلَكُمُ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ لَوَلَّوُا۟ ٱلْأَدْبَٰرَ ثُمَّ لَا يَجِدُونَ وَلِيًّا وَلَا نَصِيرًا ﴿٢٢﴾ سُنَّةَ
ٱللَّهِ ٱلَّتِى قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلُ ۖ وَلَن تَجِدَ لِسُنَّةِ ٱللَّهِ تَبْدِيلًا ﴿٢٣﴾

(16) Ka ce da waɗanda suka ƙi fita tare da kai[1] daga mutanen ƙauye: "Ba da daɗewa ba za a kirawo ku zuwa wurin wasu mutane masu tsananin yaƙi don ku yaƙe su ko su musulunta. To idan kuka bi (wannan umarni), Allah zai ba ku lada kyakkyawa, idan kuwa kuka ba da baya kamar yadda kuka ba da baya a da can, zai azabtar da ku azaba mai raɗaɗi."

(17) Babu wani laifi a kan makaho, babu kuma wani laifi a kan gurgu, kuma babu wani laifi a kan marar lafiya (game da rashin fita yaƙi). Wanda kuwa ya bi Allah da Manzonsa to zai shigar da shi gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, wanda kuma ya ba da baya to zai azabtar da shi azaba mai raɗaɗi

(18) Haƙiƙa Allah Ya yarda da muminai yayin da suke yi maka mubaya'a a ƙarƙashin bishiyar[2] nan, to Allah Ya san abin da yake cikin zukatansu, sai Ya saukar musu da nutsuwa Ya kuma saka musu da buɗi na kurkusaɓ[3]

(19) Da kuma ganimomi masu yawa da za su yi ta kwasar su. Allah kuwa Ya kasance Mabuwayi ne, Mai hikima

(20) Allah kuma Ya yi muku alƙawarin wasu ganimomi masu yawa da za ku yi ta kwasar su, sai Ya gaggauto muku da wannan (ganimar Khaibara) Ya kuma kame muku hannayen mutanen (wato Yahudu), don kuwa (wannan) ya zama aya ga muminai, Ya kuma shiryar da su hanya madaidaiciya

(21) Daya (ganimar) kuwa ba ku sami iko a kanta ba[4], haƙiƙa Allah Ya san da ita, Allah kuwa Ya kasance Mai iko ne a kan komai

(22) Da kuwa waɗanda suka kafirta za su yaƙe ku, tabbas da sun juya da baya, sannan ba za su sami wani majiɓinci ko mataimaki ba

(23) (Wannan ita ce) sunnar Allah wadda ta riga ta gabata tun tuni; ba kuwa za ka taɓa samun canji ba game da sunnar Allah

(1) Watau zuwa Makka.

(2) Su ne sahabban Annabi ( ) kimanin su dubu da xari huxu da suka yi wa Manzon Allah ( ) mubaya'a a Hudaibiyya a kan za su jajirce wajen yaqi tare da shi.

(3) Watau buxe Khaibar a madadin rashin samun shiga garin Makka su yi umara.

(4) Kamar abin da suka samu na ganimomin Farisawa da Rumawa lokacin da suka cinye su da yaqi.

وَهُوَ ٱلَّذِى كَفَّ أَيْدِيَهُمْ عَنكُمْ وَأَيْدِيَكُمْ عَنْهُم بِبَطْنِ مَكَّةَ مِنۢ
بَعْدِ أَنْ أَظْفَرَكُمْ عَلَيْهِمْ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرًا ﴿٢٤﴾
هُمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَصَدُّوكُمْ عَنِ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ
وَٱلْهَدْىَ مَعْكُوفًا أَن يَبْلُغَ مَحِلَّهُۥ ۚ وَلَوْلَا رِجَالٌ مُّؤْمِنُونَ وَنِسَآءٌ
مُّؤْمِنَٰتٌ لَّمْ تَعْلَمُوهُمْ أَن تَطَـُٔوهُمْ فَتُصِيبَكُم مِّنْهُم مَّعَرَّةٌۢ
بِغَيْرِ عِلْمٍ ۖ لِّيُدْخِلَ ٱللَّهُ فِى رَحْمَتِهِۦ مَن يَشَآءُ ۚ لَوْ تَزَيَّلُوا۟ لَعَذَّبْنَا
ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنْهُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿٢٥﴾ إِذْ جَعَلَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟
فِى قُلُوبِهِمُ ٱلْحَمِيَّةَ حَمِيَّةَ ٱلْجَٰهِلِيَّةِ فَأَنزَلَ ٱللَّهُ سَكِينَتَهُۥ
عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَعَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ وَأَلْزَمَهُمْ كَلِمَةَ ٱلتَّقْوَىٰ
وَكَانُوٓا۟ أَحَقَّ بِهَا وَأَهْلَهَا ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمًا ﴿٢٦﴾
لَّقَدْ صَدَقَ ٱللَّهُ رَسُولَهُ ٱلرُّءْيَا بِٱلْحَقِّ ۖ لَتَدْخُلُنَّ ٱلْمَسْجِدَ
ٱلْحَرَامَ إِن شَآءَ ٱللَّهُ ءَامِنِينَ مُحَلِّقِينَ رُءُوسَكُمْ وَمُقَصِّرِينَ
لَا تَخَافُونَ ۖ فَعَلِمَ مَا لَمْ تَعْلَمُوا۟ فَجَعَلَ مِن دُونِ ذَٰلِكَ
فَتْحًا قَرِيبًا ﴿٢٧﴾ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلْهُدَىٰ وَدِينِ
ٱلْحَقِّ لِيُظْهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦ ۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدًا ﴿٢٨﴾

(24) Shi ne kuma Wanda Ya kame muku hannayensu[1] , kuma (Ya kame) musu hannayenku a cikin Makka bayan kuwa Ya riga ya ba ku nasara a kansu. Allah kuma Ya zamanto Mai ganin abin da kuke aikatawa ne

(25) Su ne waɗanda suka kafirta suka kuma hana ku isa ga Masallaci mai alfarma, suka kuma hana dabbobin hadaya isa wurin yankansu. Kuma ba don wasu mazaje muminai da wasu mataye muminai da ba ku san su ba, don kada ku kashe su, sannan wani laifi nasu ya same ku ba tare da sani ba, (da Ya ba ku damar yaƙar su. Wannan ya faru ne) don Allah Ya shigar da wanda Ya ga dama cikin rahamarsa. Da sun ware to lalle da Mun azabtar da waɗanda suka kafirta daga cikinsu azaba mai tsanani

(26) Yayin da waɗanda suka kafirta suka sanya kishi irin kishin jahiliyya a cikin zukatansu, sai Allah Ya saukar da nutsuwarsa ga Manzonsa da muminai, Ya kuma kimsa musu kalmar imani[2] , da ma kuma su suka fi cancantarta, kuma (su ne) masu ita. Allah kuma Ya kasance Masanin komai ne

(27) Haƙiƙa Allah Ya tabbatar wa Manzonsa gaskiyar mafarkin cewa, lalle za ku shiga Masallaci mai alfarma insha Allahu, kuna cikin aminci kuna masu aske kawunanku da masu yin saisaye, ba tare da kuna jin tsoron (komai) ba, to Ya san abin da ba ku sani ba, sai Ya sanya budi na kusa[3] kafin wannan .

(28) Shi ne Wanda Ya aiko Manzonsa da shiriya da kuma addini na gaskiya don Ya ɗora shi a kan kowane addini. Allah kuma Ya isa Mai shaida

(1) Watau yayin da mayaqa mutum tamanin suka nufo su da Hudaibiyya da niyyar cutar da su.

(2) Watau kalmar shahada.

(3) Watau sulhul Hudaibiyya da buxe Khaibar.


مُحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِ ۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلْكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيْنَهُمْ ۖ
تَرَىٰهُمْ رُكَّعًا سُجَّدًا يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضْوَٰنًا ۖ سِيمَاهُمْ
فِى وُجُوهِهِم مِّنْ أَثَرِ ٱلسُّجُودِ ۚ ذَٰلِكَ مَثَلُهُمْ فِى ٱلتَّوْرَىٰةِ ۚ وَمَثَلُهُمْ فِى
ٱلْإِنجِيلِ كَزَرْعٍ أَخْرَجَ شَطْـَٔهُۥ فَـَٔازَرَهُۥ فَٱسْتَغْلَظَ فَٱسْتَوَىٰ
عَلَىٰ سُوقِهِۦ يُعْجِبُ ٱلزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ ٱلْكُفَّارَ ۗ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنْهُم مَّغْفِرَةً وَأَجْرًا عَظِيمًا ﴿٢٩﴾

سُورَةُ الحُجُرَاتِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تُقَدِّمُوا۟ بَيْنَ يَدَىِ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ۖ وَٱتَّقُوا۟
ٱللَّهَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿١﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَرْفَعُوٓا۟
أَصْوَٰتَكُمْ فَوْقَ صَوْتِ ٱلنَّبِىِّ وَلَا تَجْهَرُوا۟ لَهُۥ بِٱلْقَوْلِ كَجَهْرِ بَعْضِكُمْ
لِبَعْضٍ أَن تَحْبَطَ أَعْمَٰلُكُمْ وَأَنتُمْ لَا تَشْعُرُونَ ﴿٢﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ
يَغُضُّونَ أَصْوَٰتَهُمْ عِندَ رَسُولِ ٱللَّهِ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱمْتَحَنَ
ٱللَّهُ قُلُوبَهُمْ لِلتَّقْوَىٰ ۚ لَهُم مَّغْفِرَةٌ وَأَجْرٌ عَظِيمٌ ﴿٣﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ
يُنَادُونَكَ مِن وَرَآءِ ٱلْحُجُرَٰتِ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْقِلُونَ ﴿٤﴾

(29) Muhammadu Manzon Allah ne. Waɗanda kuma suke tare da shi masu tsanani ne a kan kafirai, kuma masu tausayin junansu ne; za ka gan su suna ruku'i suna sujjada suna neman falala daga Allah da yardarsa; alamominsu na gurbin sujjada suna bayyana a fuskokinsu. Wannan shi ne misalinsu a cikin Attaura. Misalinsu kuwa a cikin Linjila kamar shuka ce da ta fitar da reshenta sai ya ƙarfafe ta, sannan ta yi kauri sai ta daidaita a kan tushiyarta ta rika ƙayatar da manoma, don Ya cusa wa kafirai haushi. Allah Ya yi wa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari daga cikinsu alƙawarin gafara da lada mai girma

Sura Hujurat

(1) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku wuce gaban Allah da Manzonsa[1], kuma ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Mai ji ne, Masani
(2) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ɗaga muryoyinku sama da muryar Annabi, kada kuma ku ɗaga masa murya wajen yin magana kamar yadda shashinku yake ɗaga wa shashi, don kada ayyukanku su lalace alhali kuwa ku ba ku sani ba
(3) Lalle waɗanda suke yin ƙasa-ƙasa da muryoyinsu a wurin Manzon Allah, waɗannan su ne waɗanda Allah Ya jarrabi zukatansu da imani. Suna da (sakamakon) gafara da lada mai girma
(4) Lalle waɗanda suke kiran ka ta bayan ɗakuna[2] yawancinsu ba su da hankali

(1) Watau wajen aikata wani aiki ko faxar wata magana kafin su saurari abin da Allah da Manzonsa ( ) za su faxa.

(2) Watau xakunan matan Annabi ( ). Ana nufin mutanen qauye masu zuwa Madina wurin Annabi ( ) don wata buqata.

وَلَوْ أَنَّهُمْ صَبَرُوا۟ حَتَّىٰ تَخْرُجَ إِلَيْهِمْ لَكَانَ خَيْرًا لَّهُمْ ۚ وَٱللَّهُ غَفُورٌ
رَّحِيمٌ ﴿٥﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِن جَآءَكُمْ فَاسِقٌۢ بِنَبَإٍ فَتَبَيَّنُوٓا۟ أَن
تُصِيبُوا۟ قَوْمًۢا بِجَهَٰلَةٍ فَتُصْبِحُوا۟ عَلَىٰ مَا فَعَلْتُمْ نَٰدِمِينَ ﴿٦﴾
وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ فِيكُمْ رَسُولَ ٱللَّهِ ۚ لَوْ يُطِيعُكُمْ فِى كَثِيرٍ مِّنَ ٱلْأَمْرِ لَعَنِتُّمْ
وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ حَبَّبَ إِلَيْكُمُ ٱلْإِيمَٰنَ وَزَيَّنَهُۥ فِى قُلُوبِكُمْ وَكَرَّهَ
إِلَيْكُمُ ٱلْكُفْرَ وَٱلْفُسُوقَ وَٱلْعِصْيَانَ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلرَّٰشِدُونَ ﴿٧﴾
فَضْلًا مِّنَ ٱللَّهِ وَنِعْمَةً ۚ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿٨﴾ وَإِن طَآئِفَتَانِ
مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٱقْتَتَلُوا۟ فَأَصْلِحُوا۟ بَيْنَهُمَا ۖ فَإِنۢ بَغَتْ إِحْدَىٰهُمَا
عَلَى ٱلْأُخْرَىٰ فَقَٰتِلُوا۟ ٱلَّتِى تَبْغِى حَتَّىٰ تَفِىٓءَ إِلَىٰٓ أَمْرِ ٱللَّهِ ۚ فَإِن فَآءَتْ
فَأَصْلِحُوا۟ بَيْنَهُمَا بِٱلْعَدْلِ وَأَقْسِطُوٓا۟ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُقْسِطِينَ
﴿٩﴾ إِنَّمَا ٱلْمُؤْمِنُونَ إِخْوَةٌ فَأَصْلِحُوا۟ بَيْنَ أَخَوَيْكُمْ ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ
لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿١٠﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا يَسْخَرْ قَوْمٌ مِّن قَوْمٍ
عَسَىٰٓ أَن يَكُونُوا۟ خَيْرًا مِّنْهُمْ وَلَا نِسَآءٌ مِّن نِّسَآءٍ عَسَىٰٓ أَن يَكُنَّ خَيْرًا
مِّنْهُنَّ ۖ وَلَا تَلْمِزُوٓا۟ أَنفُسَكُمْ وَلَا تَنَابَزُوا۟ بِٱلْأَلْقَٰبِ ۖ بِئْسَ ٱلِٱسْمُ
ٱلْفُسُوقُ بَعْدَ ٱلْإِيمَٰنِ ۚ وَمَن لَّمْ يَتُبْ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿١١﴾

(5) Da za su yi haƙuri har sai ka fito wurinsu da ya fiye musu alheri. Allah kuma Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(6) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan wani fasiƙi ya zo muku da wani labari, to ku yi bincike, don kada ku cuci mutane cikin rashin sani, sannan ku wayi gari kuna masu nadama game da abin da kuka aikata

(7) Kuma ku sani cewa Manzon Allah yana cikinku. Da zai biye muku game da al'amura masu yawa, tabbas da kun wahala, sai dai kuma Allah Ya sa muku son imani Ya kuma ƙawata shi a cikin zukatanku, Ya kuma sa muku ƙin kafirci da fasiƙanci da saɓo. Waɗannan su ne shiryayyu

(8) (Wannan) falala ce daga Allah da kuma ni'ima, Allah kuwa Masani ne, Mai hikima

(9) Idan kuma wasu ƙungiyoyi biyu na muminai suka yaƙi junansu sai ku yi sulhu a tsakaninsu; to idan ɗayarsu ta yi ta'adda a kan ɗayar, to sai ku yaƙi wadda ta yi ta'addar har sai ta komo zuwa bin umarnin Allah. Idan ta komo sai ku yi sulhu a tsakaninsu bisa adalci, ku kuma yi adalci; lalle Allah Yana son masu adalci

(10) Lalle muminai 'yan'uwan juna ne, sai ku yi sulhu a tsakanin 'yan'uwanku. Kuma ku kiyaye dokokin Allah don a ji ƙan ku

(11) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada wasu mutane su yi wa wasu mutane izgili, mai yiwuwa ne su zamanto sun fi su alheri, kuma kada wasu mata (su yi wa) wasu mata (izgili), mai yiwuwa ne su zamanto sun fi su alheri; kada kuma ku riƙa aibata junanku, kuma kada ku riƙa jifan juna da munanan laƙuba (da kuke ƙi). Tir da sunan fasiƙanci bayan imani. Wanda duk bai tuba ba, to waɗannan su ne azzalumai

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱجْتَنِبُواْ كَثِيرًا مِّنَ ٱلظَّنِّ إِنَّ بَعْضَ ٱلظَّنِّ
إِثْمٌ ۖ وَلَا تَجَسَّسُواْ وَلَا يَغْتَب بَّعْضُكُم بَعْضًا ۚ أَيُحِبُّ أَحَدُكُمْ أَن
يَأْكُلَ لَحْمَ أَخِيهِ مَيْتًا فَكَرِهْتُمُوهُ ۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ
تَوَّابٌ رَّحِيمٌ ﴿١٢﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّا خَلَقْنَٰكُم مِّن ذَكَرٍ وَأُنثَىٰ وَجَعَلْنَٰكُمْ
شُعُوبًا وَقَبَآئِلَ لِتَعَارَفُوٓاْ ۚ إِنَّ أَكْرَمَكُمْ عِندَ ٱللَّهِ أَتْقَىٰكُمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ
عَلِيمٌ خَبِيرٌ ﴿١٣﴾ * قَالَتِ ٱلْأَعْرَابُ ءَامَنَّا ۖ قُل لَّمْ تُؤْمِنُواْ وَلَٰكِن
قُولُوٓاْ أَسْلَمْنَا وَلَمَّا يَدْخُلِ ٱلْإِيمَٰنُ فِى قُلُوبِكُمْ ۖ وَإِن تُطِيعُواْ ٱللَّهَ
وَرَسُولَهُۥ لَا يَلِتْكُم مِّنْ أَعْمَٰلِكُمْ شَيْـًٔا ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٤﴾
إِنَّمَا ٱلْمُؤْمِنُونَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ثُمَّ لَمْ يَرْتَابُواْ
وَجَٰهَدُواْ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ
ٱلصَّٰدِقُونَ ﴿١٥﴾ قُلْ أَتُعَلِّمُونَ ٱللَّهَ بِدِينِكُمْ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ مَا فِى
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۚ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿١٦﴾ يَمُنُّونَ
عَلَيْكَ أَنْ أَسْلَمُواْ ۖ قُل لَّا تَمُنُّواْ عَلَىَّ إِسْلَٰمَكُم ۖ بَلِ ٱللَّهُ يَمُنُّ
عَلَيْكُمْ أَنْ هَدَىٰكُمْ لِلْإِيمَٰنِ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿١٧﴾ إِنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ
غَيْبَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ وَٱللَّهُ بَصِيرٌۢ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿١٨﴾

(12) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku nisanci yawancin zace-zace, lalle shashin zace-zace laifi ne; kada kuma ku rika binciken laifukan wasu, kuma kada shashinku ya rika gibar shashi. Yanzu ɗayanku zai so ya ci naman ɗan'uwansa matacce? To sai kuka ƙi shi. To ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Mai karɓar tuba ne, Mai jin ƙai

(13) Ya ku mutane, lalle Mu Muka halicce ku daga namiji da mace, Muka kuma sanya ku al'ummu da ƙabilu don ku san juna. Lalle mafi girmanku a wurin Allah shi ne wanda ya fi ku taƙawa. Lalle Allah Masanin sarari ne, Masanin ɓoye

(14) (Larabawa) ƙauyawa suka ce: "Mun yi imani." Ka ce: "Ba ku yi imani ba, sai dai ku ce 'mun musulunta', don kuwa imani bai riga ya shiga zukatanku ba; idan kuwa kuka bi Allah da Manzonsa, to ba zai tauye muku wani abu daga (ladan) ayyukanku ba. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai rahama."

(15) Muminai kawai su ne waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, sannan ba su yi kokwanto ba, suka kuma yi yaƙi da dukiyoyinsu da rayukansu a hanyar Allah, Waɗannan su ne masu gaskiya

(16) Ka ce: "Yanzu kwa rika sanar da Allah addininku, alhali kuwa Allah Yana sane da abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa? Allah kuwa Masanin komai ne."

(17) Suna yi maka gorin sun musulunta; ka ce: "Kada ku yi min gorin musuluntarku; a'a, Allah ne ma zai yi muku gori don Ya shiryar da ku zuwa ga imani, idan kun kasance masu gaskiya."

(18) Lalle Allah Yana sane da abin da yake ɓoye a sammai da ƙasa, Allah kuma Mai ganin abin da kuke aikatawa ne

Sura Kaf

سُورَةُ قٓ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قٓۚ وَٱلۡقُرۡءَانِ ٱلۡمَجِيدِ ١ بَلۡ عَجِبُوٓاْ أَن جَآءَهُم مُّنذِرٞ مِّنۡهُمۡ
فَقَالَ ٱلۡكَٰفِرُونَ هَٰذَا شَيۡءٌ عَجِيبٌ ٢ أَءِذَا مِتۡنَا وَكُنَّا تُرَابٗاۖ ذَٰلِكَ
رَجۡعُۢ بَعِيدٞ ٣ قَدۡ عَلِمۡنَا مَا تَنقُصُ ٱلۡأَرۡضُ مِنۡهُمۡۖ وَعِندَنَا كِتَٰبٌ
حَفِيظُۢ ٤ بَلۡ كَذَّبُواْ بِٱلۡحَقِّ لَمَّا جَآءَهُمۡ فَهُمۡ فِيٓ أَمۡرٖ مَّرِيجٍ ٥
أَفَلَمۡ يَنظُرُوٓاْ إِلَى ٱلسَّمَآءِ فَوۡقَهُمۡ كَيۡفَ بَنَيۡنَٰهَا وَزَيَّنَّٰهَا
وَمَا لَهَا مِن فُرُوجٖ ٦ وَٱلۡأَرۡضَ مَدَدۡنَٰهَا وَأَلۡقَيۡنَا فِيهَا رَوَٰسِيَ
وَأَنۢبَتۡنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوۡجِۭ بَهِيجٖ ٧ تَبۡصِرَةٗ وَذِكۡرَىٰ لِكُلِّ عَبۡدٖ
مُّنِيبٖ ٨ وَنَزَّلۡنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ مُّبَٰرَكٗا فَأَنۢبَتۡنَا بِهِۦ جَنَّٰتٖ
وَحَبَّ ٱلۡحَصِيدِ ٩ وَٱلنَّخۡلَ بَاسِقَٰتٖ لَّهَا طَلۡعٞ نَّضِيدٞ ١٠ رِّزۡقٗا
لِّلۡعِبَادِۖ وَأَحۡيَيۡنَا بِهِۦ بَلۡدَةٗ مَّيۡتٗاۚ كَذَٰلِكَ ٱلۡخُرُوجُ ١١ كَذَّبَتۡ قَبۡلَهُمۡ
قَوۡمُ نُوحٖ وَأَصۡحَٰبُ ٱلرَّسِّ وَثَمُودُ ١٢ وَعَادٞ وَفِرۡعَوۡنُ وَإِخۡوَٰنُ
لُوطٖ ١٣ وَأَصۡحَٰبُ ٱلۡأَيۡكَةِ وَقَوۡمُ تُبَّعٖۚ كُلّٞ كَذَّبَ ٱلرُّسُلَ فَحَقَّ وَعِيدِ
١٤ أَفَعَيِينَا بِٱلۡخَلۡقِ ٱلۡأَوَّلِۚ بَلۡ هُمۡ فِي لَبۡسٖ مِّنۡ خَلۡقٖ جَدِيدِۢ ١٥

(1) Kaf[1] Na rantse da Alƙur'ani mai girma (2) A'a, sun dai yi mamakin cewa, wani mai gargaɗi daga cikinsu ya zo musu, sai kafirai suka ce: "Wannan abu ne mai ban mamaki!(3) "Yanzu idan muka mutu muka zama ƙasa, (a ce za a komo da mu)? Wannan komowa ce mai nisa!"(4) Haƙiƙa Mun san abin da ƙasa take cinyewa daga gare su; a wurinmu kuma akwai wani littafi mai kiyayewa[2] (5) A'a, sun dai ƙaryata gaskiya ne lokacin da ta zo musu, don haka suna cikin al'amari rikitacce[3] . (6) Yanzu ba sa duban sama da take sama da su (su ga) yadda Muka gina ta, Muka kuma ƙawata ta, ba ta kuma da wasu tsage-tsage?
(7) Kasa kuma Muka shimfiɗa ta, Muka kuma sanya turaku a cikinta, Muka kuma tsirar da kowane irin nau'in (tsiro) mai ƙayatarwa a cikinta
(8)Don jan hankali da wa'azantarwa ga duk wani bawa mai mayar da al'amarinsa ga Allah(9) Muka kuma saukar da ruwa mai albarka daga sama sai Muka tsiro da lambuna da shi da kuma ƙwayoyin da ake girba
(10) Da kuma itatuwan dabinai dogwaye da suke da 'ya'ya dodo-dodo (11) Don arzuta bayi, Muka kuma raya busasshen gari da shi. Kamar haka ne fitowa (daga ƙabari) take
(12) Mutanen Nuhu da ma'abota rijiyar Rassu da Samudawa (duka) sun ƙaryata (annabawa) a gabaninsu (watau mutanen Makka)
(13) Da kuma Adawa da Fir'auna da 'yan'uwan Luɗu (su ma sun ƙaryata)
(14) Da kuma ma'abota surƙuƙi[4] da mutanen Tubba'u[5]. Kowannensu ya ƙaryata manzanni, sai azabata ta tabbata (a kansu)
(15) Shin Mun gaza ne da halittar farko? A'a, su dai suna cikin shakka ne game da sake halitta

(1) Duba Suratul Baqara, aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Watau Lauhul Mahfuz.

(3) Watau game da Manzon Allah ( ), wani lokaci su ce matsafi ne, wani lokaci kuma su ce boka ne, wani lokaci kuma su ce mawaqi ne.

(4) Watau mutanen Annabi Shu'aibu ( ).

(5) Tubba'u shi ne sarkin Yaman

وَلَقَدْ خَلَقْنَا ٱلْإِنسَٰنَ وَنَعْلَمُ مَا تُوَسْوِسُ بِهِۦ نَفْسُهُۥ ۖ وَنَحْنُ أَقْرَبُ إِلَيْهِ
مِنْ حَبْلِ ٱلْوَرِيدِ ﴿١٦﴾ إِذْ يَتَلَقَّى ٱلْمُتَلَقِّيَانِ عَنِ ٱلْيَمِينِ وَعَنِ ٱلشِّمَالِ
قَعِيدٌ ﴿١٧﴾ مَّا يَلْفِظُ مِن قَوْلٍ إِلَّا لَدَيْهِ رَقِيبٌ عَتِيدٌ ﴿١٨﴾ وَجَآءَتْ سَكْرَةُ
ٱلْمَوْتِ بِٱلْحَقِّ ۖ ذَٰلِكَ مَا كُنتَ مِنْهُ تَحِيدُ ﴿١٩﴾ وَنُفِخَ فِى ٱلصُّورِ ۚ ذَٰلِكَ
يَوْمُ ٱلْوَعِيدِ ﴿٢٠﴾ وَجَآءَتْ كُلُّ نَفْسٍ مَّعَهَا سَآئِقٌ وَشَهِيدٌ ﴿٢١﴾ لَّقَدْ
كُنتَ فِى غَفْلَةٍ مِّنْ هَٰذَا فَكَشَفْنَا عَنكَ غِطَآءَكَ فَبَصَرُكَ ٱلْيَوْمَ حَدِيدٌ
﴿٢٢﴾ وَقَالَ قَرِينُهُۥ هَٰذَا مَا لَدَىَّ عَتِيدٌ ﴿٢٣﴾ أَلْقِيَا فِى جَهَنَّمَ كُلَّ كَفَّارٍ
عَنِيدٍ ﴿٢٤﴾ مَّنَّاعٍ لِّلْخَيْرِ مُعْتَدٍ مُّرِيبٍ ﴿٢٥﴾ ٱلَّذِى جَعَلَ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا
ءَاخَرَ فَأَلْقِيَاهُ فِى ٱلْعَذَابِ ٱلشَّدِيدِ ﴿٢٦﴾ ۞ قَالَ قَرِينُهُۥ رَبَّنَا مَآ أَطْغَيْتُهُۥ
وَلَٰكِن كَانَ فِى ضَلَٰلٍۭ بَعِيدٍ ﴿٢٧﴾ قَالَ لَا تَخْتَصِمُوا۟ لَدَىَّ وَقَدْ قَدَّمْتُ
إِلَيْكُم بِٱلْوَعِيدِ ﴿٢٨﴾ مَا يُبَدَّلُ ٱلْقَوْلُ لَدَىَّ وَمَآ أَنَا۠ بِظَلَّٰمٍ لِّلْعَبِيدِ ﴿٢٩﴾
يَوْمَ نَقُولُ لِجَهَنَّمَ هَلِ ٱمْتَلَأْتِ وَتَقُولُ هَلْ مِن مَّزِيدٍ ﴿٣٠﴾ وَأُزْلِفَتِ
ٱلْجَنَّةُ لِلْمُتَّقِينَ غَيْرَ بَعِيدٍ ﴿٣١﴾ هَٰذَا مَا تُوعَدُونَ لِكُلِّ أَوَّابٍ حَفِيظٍ
﴿٣٢﴾ مَّنْ خَشِىَ ٱلرَّحْمَٰنَ بِٱلْغَيْبِ وَجَآءَ بِقَلْبٍ مُّنِيبٍ ﴿٣٣﴾ ٱدْخُلُوهَا
بِسَلَٰمٍ ۖ ذَٰلِكَ يَوْمُ ٱلْخُلُودِ ﴿٣٤﴾ لَهُم مَّا يَشَآءُونَ فِيهَا وَلَدَيْنَا مَزِيدٌ ﴿٣٥﴾

(16) Hakika kuma Mun halicci mutum, kuma Mun san abin da ransa yake saka masa; kuma Mu Muka fi kusa da shi fiye da jijiyar wuyansa (17) Yayin da (mala'iku biyu) masu hadduwa suka hadu ta dama da ta hagu suna zaune(18) Ba wata magana da zai furta face a tare da shi akwai (mala'ika) mai kula kuma halartacce
(19) Kuma magagin mutuwa ya zo da gaskiya; wannan ne abin da ka kasance kana kakkauce wa. (20) Aka kuma yi busa a ƙaho[1]. Wannan ita ce ranar narko(21) Kuma kowane rai ya zo a tare da shi akwai mai kora da mai shaida[2]

(22) Hakika ka kasance a cikin gafala game da wannan, sai Muka yaye maka yanarka, to ganinka a yau tangaran yake(23) Hakika ka kasance a cikin gafala game da wannan, sai Muka yaye maka yanarka, to ganinka a yau tangaran yake (24) (Aka ce da mala'ikun): "Ku jefa duk wani kafiri mai taurin kai cikin Jahannama (25) "Mai yawan hana alheri, mai ta'addanci, mai shakka (26) "Wanda ya sanya wani abin bauta daban tare da Allah, saboda haka ku jefa shi cikin azaba mai tsanani." (27) Shaidaninsa ya ce: "Ya Ubangijina, ni ban batar da shi ba, sai dai kawai ya kasance cikin bata mai nisa."(28) (Allah) ya ce: "Kada ku yi husuma a gabana, hakika tuni Na gabatar muku da gargadin azaba (29) "Ba a sauya magana a gabana, kuma Ni ba mai zaluntar bayi ba ne."
(30) A ranar da za Mu ce da Jahannama: "Shin kin cika?" (Ita) kuma ta ce: "Shin akwai wani ƙari?" (31)Aka kuma kusantar da Aljanna ga masu tsoron Allah, ba tare da nisa ba (32) (Sai a ce da su): "Wannan ne abin da ake yi muku alkawarinsa, (ga shi nan a tanade) ga duk wani mai yawan komawa ga Allah, mai kiyaye (dokokinsa)(33) "Wanda ya ji tsoron Allah a boye, ya zo kuma da zuciya mai komawa ga Allah."(34) (Za a ce da su): Ku shige ta da aminci; wannan ita ce ranar dawwama(35) Suna da duk abin da suka dama a cikinta, kuma wurinmu akwai wani ƙari[3]

(1) Watau busa ta biyu.

(2) Watau mala'iku biyu tare da kowane mutum, xaya yana kora shi; xaya kuma mai ba da shaida game da shi.

(3) Watau qarin wasu ni'imomi, daga cikinsu akwai ganin Fuskar Allah da samun yardarsa ta har abada.

وَكَمْ أَهْلَكْنَا قَبْلَهُم مِّن قَرْنٍ هُمْ أَشَدُّ مِنْهُم بَطْشًا فَنَقَّبُوا۟
فِى ٱلْبِلَٰدِ هَلْ مِن مَّحِيصٍ ﴿٣٦﴾ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَذِكْرَىٰ لِمَن
كَانَ لَهُۥ قَلْبٌ أَوْ أَلْقَى ٱلسَّمْعَ وَهُوَ شَهِيدٌ ﴿٣٧﴾ وَلَقَدْ خَلَقْنَا
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ وَمَا مَسَّنَا
مِن لُّغُوبٍ ﴿٣٨﴾ فَٱصْبِرْ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ
قَبْلَ طُلُوعِ ٱلشَّمْسِ وَقَبْلَ ٱلْغُرُوبِ ﴿٣٩﴾ وَمِنَ ٱلَّيْلِ فَسَبِّحْهُ
وَأَدْبَٰرَ ٱلسُّجُودِ ﴿٤٠﴾ وَٱسْتَمِعْ يَوْمَ يُنَادِ ٱلْمُنَادِ مِن مَّكَانٍ قَرِيبٍ
﴿٤١﴾ يَوْمَ يَسْمَعُونَ ٱلصَّيْحَةَ بِٱلْحَقِّ ذَٰلِكَ يَوْمُ ٱلْخُرُوجِ ﴿٤٢﴾ إِنَّا
نَحْنُ نُحْىِۦ وَنُمِيتُ وَإِلَيْنَا ٱلْمَصِيرُ ﴿٤٣﴾ يَوْمَ تَشَقَّقُ ٱلْأَرْضُ
عَنْهُمْ سِرَاعًا ذَٰلِكَ حَشْرٌ عَلَيْنَا يَسِيرٌ ﴿٤٤﴾ نَّحْنُ أَعْلَمُ بِمَا يَقُولُونَ
وَمَآ أَنتَ عَلَيْهِم بِجَبَّارٍ فَذَكِّرْ بِٱلْقُرْءَانِ مَن يَخَافُ وَعِيدِ ﴿٤٥﴾

سُورَةُ الذَّارِيَاتِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلذَّٰرِيَٰتِ ذَرْوًا ﴿١﴾ فَٱلْحَٰمِلَٰتِ وِقْرًا ﴿٢﴾ فَٱلْجَٰرِيَٰتِ يُسْرًا ﴿٣﴾
فَٱلْمُقَسِّمَٰتِ أَمْرًا ﴿٤﴾ إِنَّمَا تُوعَدُونَ لَصَادِقٌ ﴿٥﴾ وَإِنَّ ٱلدِّينَ لَوَٰقِعٌ ﴿٦﴾

(36) Al'ummu nawa Muka hallaka a gabaninsu waɗanda suka fi su tsananin ƙarfi, sai suka riƙa bincike cikin garuruwa ko akwai wata matsera
(37) Lalle game da wannan tabbas akwai wa'azi ga wanda ya kasance yana da hankali ko kuma ya karkaɗe kunne (don sauraron wa'azi), alhali zuciyarsa tana tare da shi
(38) Haƙiƙa kuma Mun halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu cikin kwana shida, kuma wata gajiya ba ta shafe mu ba
(39) To ka yi haƙuri a kan abin da suke faɗa, ka kuma yi tasbihi da yabon Ubangijinka kafin fudowar rana da kuma kafin faɗuwarta
(40) Da daddare kuma sai ka tsarkake shi, da kuma bayan salloli (41) Ka kuma saurara ranar da mai kira zai yi kira[1] daga wani wuri makusanci (42) A ranar da (talikai) za su ji tsawa ta gaskiya[2]. Wannan ita ce ranar fitowa (daga ƙabari) (43) Lalle Mu ne Muke rayawa, Muke kuma kashewa, kuma makoma zuwa gare Mu ne (44) A ranar da ƙasa za ta tsattsage musu (su fito) da gaggawa. Wannan tattarawa ce mai sauƙi a gare Mu (45) Mu ne Muka fi sanin abin da (kafiran Makka) suke faɗa; kuma kai ba mai tilasta musu ba ne; saboda haka sai ka yi wa'azi da Alƙur'ani ga wanda yake tsoron azabata

Sura Zariyat

(1) Na rantse da iskoki masu ta da ƙura
(2) Sannan da (giragizai) waɗanda suke ɗauke da nauyin ruwa
(3) Da jiragen ruwa masu gudu a sauƙaƙe
(4) Da kuma mala'iku masu raba abubuwa
(5) Lalle abin da ake yi muku alƙawarinsa tabbas gaskiya ne
(6) Kuma lalle sakamako tabbas mai afkuwa ne

(1) Watau mala'ikan da aka wakilta domin busa qaho.


(2) Watau busa ta biyu.

وَٱلسَّمَآءِ ذَاتِ ٱلْحُبُكِ ﴿٧﴾ إِنَّكُمْ لَفِى قَوْلٍ مُّخْتَلِفٍ ﴿٨﴾ يُؤْفَكُ عَنْهُ مَنْ
أُفِكَ ﴿٩﴾ قُتِلَ ٱلْخَرَّٰصُونَ ﴿١٠﴾ ٱلَّذِينَ هُمْ فِى غَمْرَةٍ سَاهُونَ ﴿١١﴾ يَسْـَٔلُونَ
أَيَّانَ يَوْمُ ٱلدِّينِ ﴿١٢﴾ يَوْمَ هُمْ عَلَى ٱلنَّارِ يُفْتَنُونَ ﴿١٣﴾ ذُوقُوا۟ فِتْنَتَكُمْ
هَٰذَا ٱلَّذِى كُنتُم بِهِۦ تَسْتَعْجِلُونَ ﴿١٤﴾ إِنَّ ٱلْمُتَّقِينَ فِى جَنَّٰتٍ وَعُيُونٍ
﴿١٥﴾ ءَاخِذِينَ مَآ ءَاتَىٰهُمْ رَبُّهُمْ ۚ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ قَبْلَ ذَٰلِكَ مُحْسِنِينَ ﴿١٦﴾
كَانُوا۟ قَلِيلًا مِّنَ ٱلَّيْلِ مَا يَهْجَعُونَ ﴿١٧﴾ وَبِٱلْأَسْحَارِ هُمْ يَسْتَغْفِرُونَ ﴿١٨﴾
وَفِىٓ أَمْوَٰلِهِمْ حَقٌّ لِّلسَّآئِلِ وَٱلْمَحْرُومِ ﴿١٩﴾ وَفِى ٱلْأَرْضِ ءَايَٰتٌ
لِّلْمُوقِنِينَ ﴿٢٠﴾ وَفِىٓ أَنفُسِكُمْ ۚ أَفَلَا تُبْصِرُونَ ﴿٢١﴾ وَفِى ٱلسَّمَآءِ رِزْقُكُمْ
وَمَا تُوعَدُونَ ﴿٢٢﴾ فَوَرَبِّ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ إِنَّهُۥ لَحَقٌّ مِّثْلَ مَآ أَنَّكُمْ
تَنطِقُونَ ﴿٢٣﴾ هَلْ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ضَيْفِ إِبْرَٰهِيمَ ٱلْمُكْرَمِينَ ﴿٢٤﴾ إِذْ
دَخَلُوا۟ عَلَيْهِ فَقَالُوا۟ سَلَٰمًا ۖ قَالَ سَلَٰمٌ قَوْمٌ مُّنكَرُونَ ﴿٢٥﴾ فَرَاغَ إِلَىٰٓ
أَهْلِهِۦ فَجَآءَ بِعِجْلٍ سَمِينٍ ﴿٢٦﴾ فَقَرَّبَهُۥٓ إِلَيْهِمْ قَالَ أَلَا تَأْكُلُونَ
﴿٢٧﴾ فَأَوْجَسَ مِنْهُمْ خِيفَةً ۖ قَالُوا۟ لَا تَخَفْ ۖ وَبَشَّرُوهُ بِغُلَٰمٍ عَلِيمٍ ﴿٢٨﴾
فَأَقْبَلَتِ ٱمْرَأَتُهُۥ فِى صَرَّةٍ فَصَكَّتْ وَجْهَهَا وَقَالَتْ عَجُوزٌ عَقِيمٌ
﴿٢٩﴾ قَالُوا۟ كَذَٰلِكِ قَالَ رَبُّكِ ۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٣٠﴾

(7) Na rantse da sama ma'abociyar hanyoyi
(8) Lalle ku (mutanen Makka) tabbas kuna cikin magana mai sassaɓawa
(9) Ana karkatar da wanda aka karkatar daga gare shi (Annabi ko Alkur'ani)
(10) An la'anci maƙaryata[1]
(11) Waɗanda suke rafkanannu a cikin jahilci
(12) Suna tambayar yaushe ne ranar sakamako?
(13) A ranar da su za a azabtar da su kan wuta
(14) (A ce da su): "Ku ɗanɗani azabarku, wannan shi ne abin da kuka kasance kuna neman gaggautowarsa."

(15) Lalle masu taƙawa suna cikin gidajen Aljanna da idanuwan (ruwa) (16) Suna masu kwasar abin da Ubangijinsu Ya ba su. Lalle su sun zamanto kafin wannan (ranar) masu kyautata ayyuka ne (17) Sun kasance kaɗan ne na dare suke bacci[2] (18) A gefin asuba kuma su suna neman gafara (19) A cikin dukiyoyinsu kuma akwai wani haƙƙi na mai bara da mai kamewa daga yin ta (20) A cikin ƙasa kuma akwai ayoyi ga masu sakankancewa (21) Da kuma cikin kawunanku. Yanzu ba kwa lura ba? (22) A cikin sammai kuma akwai arzikinku da kuma abin da aka yi muku alkawarinsa (23) To na rantse da Ubangijin sammai da ƙasa, lalle shi (abin da ake yi muku gargaɗinsa) tabbas gaskiya ne kamar dai yadda kuke yin magana (24) Shin labarin baƙin Ibrahimu masu girma[3] ya zo maka? (25) Lokacin da suka shiga wurinsa sai suka ce: "Muna maka sallama;" ya ce: "Aminci ya tabbata gare ku, (ku) mutane ne da ba sanannu ba." (26) Sai ya saɗaɗa da sauri zuwa ga iyalinsa, sai ya zo da wani ɗan maraƙi mai mai (27) Sai ya kusanta shi gare su, ya ce: "Yanzu ba za ku ci ba?" (28) (Da suka ƙi ci) sai ya tsorata da su, suka ce: "Kada ka tsorata;" suka kuma yi masa albishir da samun yaro mai ilimi[4]
(29) Sannan sai matarsa ta gabato su cikin wata ƙara, sai ta mari fuskarta ta ce: "Yanzu tsohuwa bakarara (ita ce za ta haihu?)" (30) Suka ce, "Kamar haka Ubangijinki Ya ce, lalle Shi Mai hikima ne, Masani."

(1) Watau game da Annabi ( ) da kuma Alqur'ani.
(2) Watau sun kasance masu yawaita sallar dare.
(3) Su ne mala'iku da Allah ya aiko.
(4) Watau Annabi Ishaq ( ).


* قَالَ فَمَا خَطْبُكُمْ أَيُّهَا الْمُرْسَلُونَ ﴿٣١﴾ قَالُوا إِنَّا أُرْسِلْنَا إِلَىٰ قَوْمٍ
مُجْرِمِينَ ﴿٣٢﴾ لِنُرْسِلَ عَلَيْهِمْ حِجَارَةً مِنْ طِينٍ ﴿٣٣﴾ مُسَوَّمَةً عِنْدَ رَبِّكَ
لِلْمُسْرِفِينَ ﴿٣٤﴾ فَأَخْرَجْنَا مَنْ كَانَ فِيهَا مِنَ الْمُؤْمِنِينَ ﴿٣٥﴾ فَمَا وَجَدْنَا
فِيهَا غَيْرَ بَيْتٍ مِنَ الْمُسْلِمِينَ ﴿٣٦﴾ وَتَرَكْنَا فِيهَا آيَةً لِلَّذِينَ يَخَافُونَ
الْعَذَابَ الْأَلِيمَ ﴿٣٧﴾ وَفِي مُوسَىٰ إِذْ أَرْسَلْنَاهُ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ بِسُلْطَانٍ
مُبِينٍ ﴿٣٨﴾ فَتَوَلَّىٰ بِرُكْنِهِ وَقَالَ سَاحِرٌ أَوْ مَجْنُونٌ ﴿٣٩﴾ فَأَخَذْنَاهُ وَجُنُودَهُ
فَنَبَذْنَاهُمْ فِي الْيَمِّ وَهُوَ مُلِيمٌ ﴿٤٠﴾ وَفِي عَادٍ إِذْ أَرْسَلْنَا عَلَيْهِمُ الرِّيحَ
الْعَقِيمَ ﴿٤١﴾ مَا تَذَرُ مِنْ شَيْءٍ أَتَتْ عَلَيْهِ إِلَّا جَعَلَتْهُ كَالرَّمِيمِ ﴿٤٢﴾
وَفِي ثَمُودَ إِذْ قِيلَ لَهُمْ تَمَتَّعُوا حَتَّىٰ حِينٍ ﴿٤٣﴾ فَعَتَوْا عَنْ أَمْرِ رَبِّهِمْ
فَأَخَذَتْهُمُ الصَّاعِقَةُ وَهُمْ يَنْظُرُونَ ﴿٤٤﴾ فَمَا اسْتَطَاعُوا مِنْ قِيَامٍ
وَمَا كَانُوا مُنْتَصِرِينَ ﴿٤٥﴾ وَقَوْمَ نُوحٍ مِنْ قَبْلُ إِنَّهُمْ كَانُوا قَوْمًا
فَاسِقِينَ ﴿٤٦﴾ وَالسَّمَاءَ بَنَيْنَاهَا بِأَيْدٍ وَإِنَّا لَمُوسِعُونَ ﴿٤٧﴾ وَالْأَرْضَ
فَرَشْنَاهَا فَنِعْمَ الْمَاهِدُونَ ﴿٤٨﴾ وَمِنْ كُلِّ شَيْءٍ خَلَقْنَا زَوْجَيْنِ
لَعَلَّكُمْ تَذَكَّرُونَ ﴿٤٩﴾ فَفِرُّوا إِلَى اللَّهِ إِنِّي لَكُمْ مِنْهُ نَذِيرٌ مُبِينٌ ﴿٥٠﴾
وَلَا تَجْعَلُوا مَعَ اللَّهِ إِلَٰهًا آخَرَ إِنِّي لَكُمْ مِنْهُ نَذِيرٌ مُبِينٌ ﴿٥١﴾

(31) (Ibrahimu) ya ce: “To me yake tafe da ku, ya ku waɗannan manzanni?”
(32) Suka ce: “Lalle mu an aiko mu ne zuwa ga wasu mutane masu manyan laifuka[1]
(33) “Don mu zuba musu ƙonannun duwatsu na tabon (wuta)
(34) “Waɗanda aka yi wa alama daga wurin Ubangijinka saboda mabarnata.”
(35) Sai Muka tserar da duk wanda ya kasance a cikinta (alƙaryar) daga muminai
(36) Sai ba mu sami wani (gida) a cikinta ba in ban da gida ɗaya na Musulmi[2]
(37) Muka kuma bar aya ta wa’azi a cikinta ga waɗanda suke tsoron azaba mai raɗaɗi (38) Game da Musa kuma (akwai aya), lokacin da Muka aiko shi zuwa ga Fir’auna da hujjoji bayyanannu (39) Sai ya ba da baya shi da ƙarfin rundunarsa, ya kuma ce: “(Musa) mai sihiri ne ko mahaukaci.” (40) Saboda haka Muka kama shi tare da rundunarsa, sai Muka watsa su a cikin kogi, alhali yana mai aikata abin Allah-wadai (41) Kuma game da Adawa (akwai aya), lokacin da Muka aiko musu da iska marar alhairi (42) Ba ta barin wani abu idan ta biyo ta kansa sai ta mayar da shi kamar daddagagge ƙashi (43) Kuma game da Samudawa (akwai aya), lokacin da aka ce da su: “Ku ji daɗi zuwa wani ɗan lokaci[3].” (44) Sai suka yi tsaurin kai game da umarnin Ubangijinsu, saboda haka tsawa ta faɗa musu alhali kuwa suna kallo (45) To ba su sami damar tsayuwa ba, kuma ba su zamanto masu taimaka wa (junansu) ba (46) Kuma (Mun hallakar da) mutanen Nuhu a gabaninsu; don kuwa lalle sun kasance mutane ne fasiƙai (47) Sama kuma Mun gina ta da ƙarfi, lalle kuma Mu tabbas Masu yalwatawa ne (48) Kasa kuma Muka shimfiɗa ta, to madalla da Masu shimfiɗar (49) Daga kowane abu kuma Mun halicci nau’i biyu, don ku wa’azantu (50) To ku gudo zuwa ga Allah[4], lalle ni mai gargaɗi ne game da Shi, mai bayyana (gargaɗi) (51) Kada kuma ku sanya wani abin bauta tare da Allah; lalle ni mai gargaɗi ne game da Shi, mai bayyana (gargaɗi)

(1) Su ne mutanen Annabi Lux ( ) masu neman maza da sha’awa.
(2) Shi ne gidan Annabi Lux ( ), in ban da matarsa, ita ba ta yi imani ba.
(3) Watau wa’adin kwana uku kacal.
(4) Watau su guje wa azabarsa zuwa kyakkyawan sakamakonsa ta hanyar yi masa biyayya.

كَذَٰلِكَ مَآ أَتَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِم مِّن رَّسُولٍ إِلَّا قَالُواْ سَاحِرٌ أَوۡ مَجۡنُونٌ ﴿٥٢﴾ أَتَوَاصَوۡاْ بِهِۦۚ بَلۡ هُمۡ قَوۡمٞ طَاغُونَ ﴿٥٣﴾ فَتَوَلَّ عَنۡهُمۡ فَمَآ أَنتَ بِمَلُومٖ ﴿٥٤﴾ وَذَكِّرۡ فَإِنَّ ٱلذِّكۡرَىٰ تَنفَعُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿٥٥﴾ وَمَا خَلَقۡتُ ٱلۡجِنَّ وَٱلۡإِنسَ إِلَّا لِيَعۡبُدُونِ ﴿٥٦﴾ مَآ أُرِيدُ مِنۡهُم مِّن رِّزۡقٖ وَمَآ أُرِيدُ أَن يُطۡعِمُونِ ﴿٥٧﴾ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلرَّزَّاقُ ذُو ٱلۡقُوَّةِ ٱلۡمَتِينُ ﴿٥٨﴾ فَإِنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُواْ ذَنُوبٗا مِّثۡلَ ذَنُوبِ أَصۡحَٰبِهِمۡ فَلَا يَسۡتَعۡجِلُونِ ﴿٥٩﴾ فَوَيۡلٞ لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن يَوۡمِهِمُ ٱلَّذِي يُوعَدُونَ ﴿٦٠﴾

سُورَةُ الطُّورِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلطُّورِ ﴿١﴾ وَكِتَٰبٖ مَّسۡطُورٖ ﴿٢﴾ فِي رَقّٖ مَّنشُورٖ ﴿٣﴾ وَٱلۡبَيۡتِ ٱلۡمَعۡمُورِ ﴿٤﴾ وَٱلسَّقۡفِ ٱلۡمَرۡفُوعِ ﴿٥﴾ وَٱلۡبَحۡرِ ٱلۡمَسۡجُورِ ﴿٦﴾ إِنَّ عَذَابَ رَبِّكَ لَوَٰقِعٞ ﴿٧﴾ مَّا لَهُۥ مِن دَافِعٖ ﴿٨﴾ يَوۡمَ تَمُورُ ٱلسَّمَآءُ مَوۡرٗا ﴿٩﴾ وَتَسِيرُ ٱلۡجِبَالُ سَيۡرٗا ﴿١٠﴾ فَوَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ﴿١١﴾ ٱلَّذِينَ هُمۡ فِي خَوۡضٖ يَلۡعَبُونَ ﴿١٢﴾ يَوۡمَ يُدَعُّونَ إِلَىٰ نَارِ جَهَنَّمَ دَعّٗا ﴿١٣﴾ هَٰذِهِ ٱلنَّارُ ٱلَّتِي كُنتُم بِهَا تُكَذِّبُونَ ﴿١٤﴾

(52) Kamar haka abin yake, ba wadanda wani manzo ya zo musu a gabaninsu (mutan Makka) sai sun ce mai sihiri ne ko mahaukaci
(53) Shin wasiyya suke yi wa junansu ne game da shi? A'a, su dai mutane ne masu ƙetare iyaka
(54) Sai ka rabu da su, don kuwa kai ba abin zargi ba ne
(55) Kuma ka yi wa'azi, don ko lalle wa'azi yana amfanar muminai
(56) Ban halicci aljanu da mutane ba sai don su bauta min
(57) Ba Na neman wani arziki a wurinsu, kuma ba Na neman su ciyar da Ni
(58) Lalle Allah Shi ne Mai arzutawa, Mai tsananin ƙarfi
(59) To lalle wadanda suka zalunci (kansu) suna da wani kaso na azaba kamar kason abokansu[1], saboda haka kada su nemi gaggauto shi
(60) To tsananin azaba ya tabbata ga wadanda suka kafirta a ranar da ake alƙawarta musu

Sura Ɗur


(1) Na rantse da dutsen Ɗuri (2) Da kuma rubutaccen littafi (3) Cikin buɗaɗɗiyar takardar fata (4) Da kuma Al-Baitul-Ma'amur[2] (5) Da kuma rufi abin ɗaukakawa[3] (6) Da kuma kogi cikakke maƙil (7) Lalle azabar Ubangijinka tabbas mai aukuwa ce (8) Ba wani mai ingije ta (9) A ranar da sama za ta yi matsananciyar jujjuyawa (10) Duwatsu kuma su riƙa tafiya (suna barin wurarensu) (11) To tsananin azaba a wanan ranar ya tabbata ga masu ƙaryatawa (12) Waɗanda suke wasanni cikin ɓarna (13) A ranar da za a ingiza su zuwa ga wutar Jahannama ingizawa (14) (Za a ce da su): "Wannan ita ce wutar da kuka kasance kuna ƙaryatawa

(1) Watau kafiran farko.
(2) Shi ne xakin da ke a sama ta bakwai, wanda a koyaushe dandazon mala'iku suke raya shi da bautar Allah.
(3) Watau sama abar xaukakawa kamar rufi.

أَفَسِحْرٌ هَٰذَآ أَمْ أَنتُمْ لَا تُبْصِرُونَ ﴿١٥﴾ اصْلَوْهَا فَاصْبِرُوٓا۟
أَوْ لَا تَصْبِرُوا۟ سَوَآءٌ عَلَيْكُمْ ۖ إِنَّمَا تُجْزَوْنَ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿١٦﴾
إِنَّ ٱلْمُتَّقِينَ فِى جَنَّٰتٍ وَنَعِيمٍ ﴿١٧﴾ فَٰكِهِينَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمْ رَبُّهُمْ
وَوَقَىٰهُمْ رَبُّهُمْ عَذَابَ ٱلْجَحِيمِ ﴿١٨﴾ كُلُوا۟ وَٱشْرَبُوا۟ هَنِيٓـًٔۢا بِمَا
كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿١٩﴾ مُتَّكِـِٔينَ عَلَىٰ سُرُرٍ مَّصْفُوفَةٍ ۖ وَزَوَّجْنَٰهُم
بِحُورٍ عِينٍ ﴿٢٠﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَٱتَّبَعَتْهُمْ ذُرِّيَّتُهُم بِإِيمَٰنٍ أَلْحَقْنَا
بِهِمْ ذُرِّيَّتَهُمْ وَمَآ أَلَتْنَٰهُم مِّنْ عَمَلِهِم مِّن شَىْءٍ ۚ كُلُّ ٱمْرِئٍۭ بِمَا
كَسَبَ رَهِينٌ ﴿٢١﴾ وَأَمْدَدْنَٰهُم بِفَٰكِهَةٍ وَلَحْمٍ مِّمَّا يَشْتَهُونَ ﴿٢٢﴾
يَتَنَٰزَعُونَ فِيهَا كَأْسًا لَّا لَغْوٌ فِيهَا وَلَا تَأْثِيمٌ ﴿٢٣﴾ ۞ وَيَطُوفُ عَلَيْهِمْ
غِلْمَانٌ لَّهُمْ كَأَنَّهُمْ لُؤْلُؤٌ مَّكْنُونٌ ﴿٢٤﴾ وَأَقْبَلَ بَعْضُهُمْ عَلَىٰ
بَعْضٍ يَتَسَآءَلُونَ ﴿٢٥﴾ قَالُوٓا۟ إِنَّا كُنَّا قَبْلُ فِىٓ أَهْلِنَا مُشْفِقِينَ
﴿٢٦﴾ فَمَنَّ ٱللَّهُ عَلَيْنَا وَوَقَىٰنَا عَذَابَ ٱلسَّمُومِ ﴿٢٧﴾ إِنَّا كُنَّا
مِن قَبْلُ نَدْعُوهُ ۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْبَرُّ ٱلرَّحِيمُ ﴿٢٨﴾ فَذَكِّرْ فَمَآ أَنتَ بِنِعْمَتِ
رَبِّكَ بِكَاهِنٍ وَلَا مَجْنُونٍ ﴿٢٩﴾ أَمْ يَقُولُونَ شَاعِرٌ نَّتَرَبَّصُ بِهِۦ رَيْبَ
ٱلْمَنُونِ ﴿٣٠﴾ قُلْ تَرَبَّصُوا۟ فَإِنِّى مَعَكُم مِّنَ ٱلْمُتَرَبِّصِينَ ﴿٣١﴾

(15) “Yanzu sihiri ne wannan ko kuwa ku ne ba kwa gani?
(16) “To ku shige ta, sai ku yi haƙuri ko kada ku yi haƙuri duk ɗaya ne; ana saka muku ne kawai da abin da kuka kasance kuna aikatawa.”
(17) Lalle masu tsoron Allah suna cikin gidajen Aljanna da ni’ima
(18) Suna masu more abin da Ubangijisu Ya ba su, Ubangijinsu kuma Ya tserar da su daga azabar Jahima
(19) Ku ci ku sha cikin jin ɗaɗi saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa
(20) Kuna masu kishingiɗa a kan gadaje waɗanda aka jera su sahu-sahu; Muka kuma aura musu ‘yan matan Hurul-Ini
(21) Waɗanda kuwa suka yi imani, zuriyarsu kuma suka bi su a imani, za Mu haɗa su da zuriyarsu(1), ba kuma za Mu tauye musu komai ba na aikinsu. Kowane mutum jingina ne ga abin da ya tsuwurwurta(2)
(22) Muka kuma daɗe su da abin marmari da nama irin wanda suke sha’awa
(23) A cikinta (Aljannar) suna musayan kofuna na giya da babu wani zancen banza game da ita, kuma babu wani zunubi
(24) Wasu yara nasu kuma waɗanda suke kamar lu’u-lu’un da yake cikin kwasfa suna kaiwa da komowa a kansu
(25) Kuma shashinsu ya fuskanci shashi suna tambayar juna
(26) Suka ce: “Lalle sanda muke cikin iyalinmu (a duniya) kafin wannan, mun kasance masu tsoron azabar Allah
(27) “Sai Allah Ya yi mana baiwa ya kiyaye mu azabar wuta
(28) “Lalle mu mun kasance a da can muna bauta masa; lalle shi Mai kyautatawa ne, Mai jin ƙai.”
(29) To ka yi wa’azi, don ba za ka zama boka ba ko mahaukaci saboda ni’imar Ubangijinka
(30) A’a, cewa dai suka yi: “Shi mawaƙi ne da muke saurara masa hanyar halaka.”
(31) Ka ce, “To ku saurara, ni ma lalle ina cikin masu sauraron.”

(1) Watau sai Allah ya xaukaka darajar ‘ya’yansu don su haxu wuri guda a Aljanna, ko da kuwa ayyukan ‘ya’yan ba su kai na iyayen ba.
(2) Watau ana tsare shi don abin da ya aikata kaxai, ba za a kama shi ne da laifin wani ba.


أَمْ تَأْمُرُهُمْ أَحْلَٰمُهُم بِهَٰذَآ أَمْ هُمْ قَوْمٌ طَاغُونَ ﴿٣٢﴾ أَمْ يَقُولُونَ تَقَوَّلَهُۥ ۚ
بَل لَّا يُؤْمِنُونَ ﴿٣٣﴾ فَلْيَأْتُوا۟ بِحَدِيثٍ مِّثْلِهِۦٓ إِن كَانُوا۟ صَٰدِقِينَ
﴿٣٤﴾ أَمْ خُلِقُوا۟ مِنْ غَيْرِ شَىْءٍ أَمْ هُمُ ٱلْخَٰلِقُونَ ﴿٣٥﴾ أَمْ خَلَقُوا۟
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ ۚ بَل لَّا يُوقِنُونَ ﴿٣٦﴾ أَمْ عِندَهُمْ خَزَآئِنُ رَبِّكَ
أَمْ هُمُ ٱلْمُصَيْطِرُونَ ﴿٣٧﴾ أَمْ لَهُمْ سُلَّمٌ يَسْتَمِعُونَ فِيهِ ۖ فَلْيَأْتِ
مُسْتَمِعُهُم بِسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿٣٨﴾ أَمْ لَهُ ٱلْبَنَٰتُ وَلَكُمُ ٱلْبَنُونَ ﴿٣٩﴾
أَمْ تَسْـَٔلُهُمْ أَجْرًا فَهُم مِّن مَّغْرَمٍ مُّثْقَلُونَ ﴿٤٠﴾ أَمْ عِندَهُمُ ٱلْغَيْبُ
فَهُمْ يَكْتُبُونَ ﴿٤١﴾ أَمْ يُرِيدُونَ كَيْدًا ۖ فَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ هُمُ ٱلْمَكِيدُونَ ﴿٤٢﴾
أَمْ لَهُمْ إِلَٰهٌ غَيْرُ ٱللَّهِ ۚ سُبْحَٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٤٣﴾ وَإِن يَرَوْا۟ كِسْفًا
مِّنَ ٱلسَّمَآءِ سَاقِطًا يَقُولُوا۟ سَحَابٌ مَّرْكُومٌ ﴿٤٤﴾ فَذَرْهُمْ حَتَّىٰ يُلَٰقُوا۟
يَوْمَهُمُ ٱلَّذِى فِيهِ يُصْعَقُونَ ﴿٤٥﴾ يَوْمَ لَا يُغْنِى عَنْهُمْ كَيْدُهُمْ شَيْـًٔا
وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿٤٦﴾ وَإِنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ عَذَابًا دُونَ ذَٰلِكَ وَلَٰكِنَّ
أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٤٧﴾ وَٱصْبِرْ لِحُكْمِ رَبِّكَ فَإِنَّكَ بِأَعْيُنِنَا ۖ وَسَبِّحْ
بِحَمْدِ رَبِّكَ حِينَ تَقُومُ ﴿٤٨﴾ وَمِنَ ٱلَّيْلِ فَسَبِّحْهُ وَإِدْبَٰرَ ٱلنُّجُومِ ﴿٤٩﴾

سُورَةُ النَّجْمِ

(32) Ko kuwa hankullansu ne suke umartar su da wannan? A'a, su dai mutane ne masu tsaurin kai
(33) Ko kuwa suna cewa: "Ya ƙago shi?" A'a, su dai ba sa yin imani ne kawai
(34) To su zo da wani zance irinsa idan sun kasance masu gaskiya
(35) Ko kuwa an halicce su ne ba da wani mai halitta ba, ko kuwa su ne masu halittar (kansu)?
(36) Ko kuwa su suka halicci sammai da ƙasa? A'a, ba sa dai sakankancewa ne
(37) Ko kuwa taskokin Ubangijinka suna wurinsu ne, ko kuwa su ne masu iko?
(38) Ko kuwa suna da wani tsani ne da suke jiyo (zancen Allah) ta kansa[1]? To mai jiyowar tasu ya zo da wata hujja mabayyaniya
(39) Ko kuwa Shi ne zai zama mai 'ya'ya mata, ku kuwa ku zamanto da 'ya'ya maza?
(40) Ko kuwa kana tambayar su wani lada ne, saboda haka bashi ya yi musu nauyi?
(41) Ko kuwa sun san gaibu ne, saboda haka su ne suke rubutawa
(42) Ko kuwa suna nufin (yi maka) makirci ne? To waɗanda suka kafirce su ne waɗanda makircinsu zai kama su
(43) Ko kuwa suna da wani abin bauta ne ba Allah ba? Tsarki ya tabbata ga Allah daga abin da suke tara (Shi da shi)
(44) Da kuwa za su ga wani yanki na azaba mai faɗowa daga sama da sai su ce: "Hadari ne haɗaɗɗe."
(45) To ka rabu da su har sai sun haɗu da ranarsu wadda za a karɓi rayukansu a cikinta
(46) Ranar da makircinsu ba zai maganta musu komai ba, kuma su ba za a taimake su ba
(47) Lalle kuma waɗanda suka yi zalunci suna da wata azabar daban[2] ban da wannan (ta lahira), sai dai kuma mafi yawansu ba su sani ba
(48) Kuma ka yi haƙuri da hukuncin Ubangijika, don ko lalle kana ƙarƙashin lurarmu; kuma ka yi tasbihi da yabon Ubangijinka lokacin da za ka tashi (daga bacci)
(49) Da daddare kuma sai ka tsarkake Shi da kuma lokacin da taurari suka ba da baya

(1) Watau cewa su ne masu gaskiya, Annabi ( ) maqaryaci ne?
(2) Watau a nan duniya ta hanyar kisa a wajen yaqi ko kamu a matsayin ribatattu ko kuma azabar qabari bayan sun mutu.

Sura Najm

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلنَّجْمِ إِذَا هَوَىٰ ﴿١﴾ مَا ضَلَّ صَاحِبُكُمْ وَمَا غَوَىٰ ﴿٢﴾ وَمَا يَنطِقُ عَنِ
ٱلْهَوَىٰ ﴿٣﴾ إِنْ هُوَ إِلَّا وَحْيٌ يُوحَىٰ ﴿٤﴾ عَلَّمَهُۥ شَدِيدُ ٱلْقُوَىٰ ﴿٥﴾
ذُو مِرَّةٍ فَٱسْتَوَىٰ ﴿٦﴾ وَهُوَ بِٱلْأُفُقِ ٱلْأَعْلَىٰ ﴿٧﴾ ثُمَّ دَنَا فَتَدَلَّىٰ ﴿٨﴾
فَكَانَ قَابَ قَوْسَيْنِ أَوْ أَدْنَىٰ ﴿٩﴾ فَأَوْحَىٰٓ إِلَىٰ عَبْدِهِۦ مَآ أَوْحَىٰ ﴿١٠﴾
مَا كَذَبَ ٱلْفُؤَادُ مَا رَأَىٰٓ ﴿١١﴾ أَفَتُمَٰرُونَهُۥ عَلَىٰ مَا يَرَىٰ ﴿١٢﴾ وَلَقَدْ رَءَاهُ
نَزْلَةً أُخْرَىٰ ﴿١٣﴾ عِندَ سِدْرَةِ ٱلْمُنتَهَىٰ ﴿١٤﴾ عِندَهَا جَنَّةُ ٱلْمَأْوَىٰٓ ﴿١٥﴾
إِذْ يَغْشَى ٱلسِّدْرَةَ مَا يَغْشَىٰ ﴿١٦﴾ مَا زَاغَ ٱلْبَصَرُ وَمَا طَغَىٰ ﴿١٧﴾ لَقَدْ رَأَىٰ
مِنْ ءَايَٰتِ رَبِّهِ ٱلْكُبْرَىٰٓ ﴿١٨﴾ أَفَرَءَيْتُمُ ٱللَّٰتَ وَٱلْعُزَّىٰ ﴿١٩﴾ وَمَنَوٰةَ
ٱلثَّالِثَةَ ٱلْأُخْرَىٰٓ ﴿٢٠﴾ أَلَكُمُ ٱلذَّكَرُ وَلَهُ ٱلْأُنثَىٰ ﴿٢١﴾ تِلْكَ إِذًا قِسْمَةٌ
ضِيزَىٰٓ ﴿٢٢﴾ إِنْ هِىَ إِلَّآ أَسْمَآءٌ سَمَّيْتُمُوهَآ أَنتُمْ وَءَابَآؤُكُم مَّآ أَنزَلَ
ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلْطَٰنٍ ۚ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ وَمَا تَهْوَى ٱلْأَنفُسُ ۖ
وَلَقَدْ جَآءَهُم مِّن رَّبِّهِمُ ٱلْهُدَىٰٓ ﴿٢٣﴾ أَمْ لِلْإِنسَٰنِ مَا تَمَنَّىٰ ﴿٢٤﴾ فَلِلَّهِ
ٱلْءَاخِرَةُ وَٱلْأُولَىٰ ﴿٢٥﴾ ۞ وَكَم مِّن مَّلَكٍ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ لَا تُغْنِى
شَفَٰعَتُهُمْ شَيْـًٔا إِلَّا مِنۢ بَعْدِ أَن يَأْذَنَ ٱللَّهُ لِمَن يَشَآءُ وَيَرْضَىٰٓ ﴿٢٦﴾

(1) Na rantse da tauraro yayin da ya fadi
(2) Mutumin naku[1] bai ɓata ba, kuma bai kauce hanya ba
(3) Kuma ba ya yin magana bisa son rai
(4) Shi (Alkur'ani) ba wani abu ne ba in ban da wahayi da ake yiwo (masa)
(5) Mai tsananin ƙarfi ne (watau Jibrilu) ya koyar da shi
(6) Mai kyawawan halitta ne, sai ya daidaita
(7) Alhali kuwa shi yana a sassa na can sama
(8) Sannan sai ya kusanto, sai ya ƙara matsawa[2]
(9) Sai ya kasance kamar kusancin kamu biyu ko ƙasa da haka
(10) Sannan (Allah) Ya yiyo wahayin abin da Ya yi wahayi zuwa ga Bawansa (Ma'aiki)
(11) Zuciyar (ta Ma'aiki) ba ta yi ƙaryar abin da ta gani ba
(12) Yanzu kwa riƙa jayayya da shi kan abin da yake gani?
(13) Haƙiƙa ya gan shi (Jibrilu) a wani karon ma[3]
(14) A wurin Magaryar tuƙewa
(15) A wurinta ne Aljannar makoma take
(16) A yayin da abin da ya lulluɓe Magaryar (na ban mamaki) ya lulluɓe ta
(17) Ganin (nasa) bai karkace ba, kuma bai zarme ba
(18) Haƙiƙa ya ga wasu ayoyin Ubangijinsa manya-manya
(19) Ku ba ni labarin (gumakan) Lata da Uzza
(20) Da Manata cikon ta ukunsu
(21) Yanzu ɗa namiji zai zama naku, Shi kuma Ya tashi da 'ya mace?
(22) Idan haka ne wannan rabon na zalunci ne[4]
(23) Su ba komai ba ne face sunaye da kuka sa musu, ku da iyayenku, Allah bai saukar muku da wata hujja ba game da su. Ba abin da suke bi sai zato da son zuciya. Haƙiƙa kuwa shiriya ta zo musu daga Ubangijinsu
(24) Ko kuwa sai mutum ya sami abin da yake buri ne?
(25) To lahira da duniya duka na Allah ne
(26) Mala'iku nawa ne a cikin sammai cetonsu ba ya amfanar da komai sai da izinin Allah ga waɗanda Ya ga dama Ya kuma yarda (da shi)?

(1) Watau Annabi Muhammadu ( ).
(2) Watau Jibrilu ( ) ya kusanto Annabi ( ) ya matso kusa don yi masa wahayi.
(3) Watau lokacin Isra'i da Mi'iraji, inda ya gan shi a halittarsa ta asali.
(4) Domin ya qunshi Fifita mahaluki a kan Mahalicci.

إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِٱلْءَاخِرَةِ لَيُسَمُّونَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةَ تَسْمِيَةَ ٱلْأُنثَىٰ ﴿٢٧﴾
وَمَا لَهُم بِهِۦ مِنْ عِلْمٍ ۖ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ ۖ وَإِنَّ ٱلظَّنَّ لَا يُغْنِى مِنَ
ٱلْحَقِّ شَيْـًٔا ﴿٢٨﴾ فَأَعْرِضْ عَن مَّن تَوَلَّىٰ عَن ذِكْرِنَا وَلَمْ يُرِدْ إِلَّا ٱلْحَيَوٰةَ
ٱلدُّنْيَا ﴿٢٩﴾ ذَٰلِكَ مَبْلَغُهُم مِّنَ ٱلْعِلْمِ ۚ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعْلَمُ بِمَن ضَلَّ عَن
سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعْلَمُ بِمَنِ ٱهْتَدَىٰ ﴿٣٠﴾ وَلِلَّهِ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى
ٱلْأَرْضِ لِيَجْزِىَ ٱلَّذِينَ أَسَـٰٓـُٔوا۟ بِمَا عَمِلُوا۟ وَيَجْزِىَ ٱلَّذِينَ أَحْسَنُوا۟
بِٱلْحُسْنَى ﴿٣١﴾ ٱلَّذِينَ يَجْتَنِبُونَ كَبَٰٓئِرَ ٱلْإِثْمِ وَٱلْفَوَٰحِشَ إِلَّا ٱللَّمَمَ ۚ
إِنَّ رَبَّكَ وَٰسِعُ ٱلْمَغْفِرَةِ ۚ هُوَ أَعْلَمُ بِكُمْ إِذْ أَنشَأَكُم مِّنَ ٱلْأَرْضِ
وَإِذْ أَنتُمْ أَجِنَّةٌ فِى بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمْ ۖ فَلَا تُزَكُّوٓا۟ أَنفُسَكُمْ ۖ هُوَ أَعْلَمُ
بِمَنِ ٱتَّقَىٰٓ ﴿٣٢﴾ أَفَرَءَيْتَ ٱلَّذِى تَوَلَّىٰ ﴿٣٣﴾ وَأَعْطَىٰ قَلِيلًا وَأَكْدَىٰٓ
﴿٣٤﴾ أَعِندَهُۥ عِلْمُ ٱلْغَيْبِ فَهُوَ يَرَىٰٓ ﴿٣٥﴾ أَمْ لَمْ يُنَبَّأْ بِمَا فِى صُحُفِ
مُوسَىٰ ﴿٣٦﴾ وَإِبْرَٰهِيمَ ٱلَّذِى وَفَّىٰٓ ﴿٣٧﴾ أَلَّا تَزِرُ وَازِرَةٌ وِزْرَ أُخْرَىٰ
﴿٣٨﴾ وَأَن لَّيْسَ لِلْإِنسَٰنِ إِلَّا مَا سَعَىٰ ﴿٣٩﴾ وَأَنَّ سَعْيَهُۥ سَوْفَ يُرَىٰ
﴿٤٠﴾ ثُمَّ يُجْزَىٰهُ ٱلْجَزَآءَ ٱلْأَوْفَىٰ ﴿٤١﴾ وَأَنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ ٱلْمُنتَهَىٰ ﴿٤٢﴾
وَأَنَّهُۥ هُوَ أَضْحَكَ وَأَبْكَىٰ ﴿٤٣﴾ وَأَنَّهُۥ هُوَ أَمَاتَ وَأَحْيَا ﴿٤٤﴾

(27) Lalle waɗanda ba sa yin imani da ranar lahira suna kiran mala’iku da sunan mata
(28) Kuma ba su da wani ilimi game da haka; ba abin da suke bi sai zato; shi kuma zato, lalle ba ya wadatar da komai game da gaskiya
(29) Sai ka kau da kai daga duk wanda ya ba da baya daga ambatonmu, bai kuma yi nufin komai ba sai rayuwar duniya
(30) Wannan ne mafkurar iliminsu. Lalle Ubangijinka Shi ne Ya fi sanin wanda ya ɓace daga hanyarsa kuma Shi Ya fi sanin wanda ya shiriya
(31) Kuma abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa na Allah ne, don Ya saka wa waɗanda suka munana da irin abin da suka aikata, Ya kuma saka wa waɗanda suka kyautata da mafi kyan sakamako
(32) (Su ne) waɗanda suke nisantar manya-manyan zunubai da munanan ayyukan saɓo, sai dai ‘yan ƙananan zunubai. Lalle Ubangijinka Mayalwacin gafara ne. Shi ne Ya fi sanin ku, tun sanda Ya halicce ku daga ƙasa, sai ga ku kun zama ‘yan tayi a cikin cikin iyayenku mata; to kada ku tsarkake kanku; Shi ne Ya fi sanin wanda ya fi taƙawa
(33) Ka ba ni labarin wanda ya ba da baya
(34) Ya kuma bayar da dukiya kaɗan kuma ya yi rowa
(35) Shin yana da ilimin gaibu ne don haka yana ganin (komai)?
(36) Ko ba a ba shi labarin abin da yake cikin takardun Musa ba ne?
(37) Da kuma Ibrahimu wanda ya cika alƙawari?
(38) Cewa: “Wani rai ba ya ɗaukar nauyin laifin wani
(39) “Kuma mutum bai mallaki wani sakamako ba sai na abin da ya aikata
(40) “Kuma lalle aikin nasa ba da daɗewa ba za a gan shi
(41) “Sannan a saka masa da cikakken sakamako
(42) “Lalle kuma zuwa ga Ubangijinka ne makoma
(43) “Kuma lalle Shi ne Ya sa a yi dariya, kuma Ya sa a yi kuka
(44) “Kuma lalle Shi ne Ya kashe kuma Ya raya

وَأَنَّهُۥ خَلَقَ ٱلزَّوْجَيْنِ ٱلذَّكَرَ وَٱلْأُنثَىٰ ﴿٤٥﴾ مِن نُّطْفَةٍ إِذَا تُمْنَىٰ
﴿٤٦﴾ وَأَنَّ عَلَيْهِ ٱلنَّشْأَةَ ٱلْأُخْرَىٰ ﴿٤٧﴾ وَأَنَّهُۥ هُوَ أَغْنَىٰ وَأَقْنَىٰ ﴿٤٨﴾ وَأَنَّهُۥ
هُوَ رَبُّ ٱلشِّعْرَىٰ ﴿٤٩﴾ وَأَنَّهُۥ أَهْلَكَ عَادًا ٱلْأُولَىٰ ﴿٥٠﴾ وَثَمُودَا۟ فَمَآ
أَبْقَىٰ ﴿٥١﴾ وَقَوْمَ نُوحٍ مِّن قَبْلُ ۖ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ هُمْ أَظْلَمَ وَأَطْغَىٰ
﴿٥٢﴾ وَٱلْمُؤْتَفِكَةَ أَهْوَىٰ ﴿٥٣﴾ فَغَشَّىٰهَا مَا غَشَّىٰ ﴿٥٤﴾ فَبِأَىِّ ءَالَآءِ
رَبِّكَ تَتَمَارَىٰ ﴿٥٥﴾ هَٰذَا نَذِيرٌ مِّنَ ٱلنُّذُرِ ٱلْأُولَىٰٓ ﴿٥٦﴾ أَزِفَتِ ٱلْآزِفَةُ
﴿٥٧﴾ لَيْسَ لَهَا مِن دُونِ ٱللَّهِ كَاشِفَةٌ ﴿٥٨﴾ أَفَمِنْ هَٰذَا ٱلْحَدِيثِ
تَعْجَبُونَ ﴿٥٩﴾ وَتَضْحَكُونَ وَلَا تَبْكُونَ ﴿٦٠﴾ وَأَنتُمْ سَٰمِدُونَ
﴿٦١﴾ فَٱسْجُدُوا۟ لِلَّهِ وَٱعْبُدُوا۟ ۩ ﴿٦٢﴾

سُورَةُ القَمَرِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱقْتَرَبَتِ ٱلسَّاعَةُ وَٱنشَقَّ ٱلْقَمَرُ ﴿١﴾ وَإِن يَرَوْا۟ ءَايَةً يُعْرِضُوا۟ وَيَقُولُوا۟
سِحْرٌ مُّسْتَمِرٌّ ﴿٢﴾ وَكَذَّبُوا۟ وَٱتَّبَعُوٓا۟ أَهْوَآءَهُمْ ۚ وَكُلُّ أَمْرٍ مُّسْتَقِرٌّ ﴿٣﴾
وَلَقَدْ جَآءَهُم مِّنَ ٱلْأَنۢبَآءِ مَا فِيهِ مُزْدَجَرٌ ﴿٤﴾ حِكْمَةٌۢ بَٰلِغَةٌ ۖ فَمَا تُغْنِ
ٱلنُّذُرُ ﴿٥﴾ فَتَوَلَّ عَنْهُمْ ۘ يَوْمَ يَدْعُ ٱلدَّاعِ إِلَىٰ شَىْءٍ نُّكُرٍ ﴿٦﴾

(45) “Kuma lalle Shi ne Ya halicci dangi biyu namiji da mace
(46) “Daga maniyyi yayin da ake zuba shi
(47) “Kuma lalle Ya ɗora wa kansa sake tashin matattu
(48) “Lalle kuma Shi ne Ya wadata, Ya kuma yalwata
(49) “Kuma lalle Shi ne Ubangijin tauraron nan Shi’ira
(50) “Lalle kuma Ya hallakar da Adawa na farko
(51) “Da kuma Samudawa, don haka bai bar saura ba
(52) “Da mutanen Nuhu tun kafin su; lalle su sun kasance su ne mafiya zalunci kuma mafiya ɗagawa
(53) “Da waɗanda aka kife (mutanen Luɗu, Allah) ya ƙaskanta su
(54) “Sannan abin da ya lulluɓe su (na azaba) ya lulluɓe su.” (55) To (kai ɗan’adam) da waɗanne ni’imomin Ubangijinka kake jayayya? (56) Wannan mai gargaɗi ne daga irin masu gargaɗin farko (57) Mai kusantowa ta kusanto (watau alƙiyama) (58) Ba wani mai bayyana lokacinta in ban da Allah (59) Yanzu game da wannan zancen ne[1] kuke mamaki? (60) Kuke kuma dariya ba kwa yin kuka? (61) Alhali kuna cikin gafala? (62) To ku yi sujjada ga Allah ku kuma bauta (masa)

Sura Kamar

(1) Alƙiyama ta kusanto, wata kuma ya tsage[2]
(2) Idan kuma suka ga wata aya sai su kau da kai kuma su ce: “Wannan sihiri ne ƙaƙƙarfa.”
(3) Suka kuma ƙaryata, suka bi soye-soyen zukatansu. Kowane al’amari kuwa (na alheri ko na sharri) mai tabbata ne
(4) Haƙiƙa kuma wasu labarai waɗanda tsawatarwa take cikinsu sun zo musu
(5) Hikima ce mai kaiwa matuƙa, sai dai kuma gargaɗin ba ya amfanarwa
(6) Saboda haka ka rabu da su. A ranar da mai kira[3] zai yi kira zuwa ga wani abu na ƙi a rai[4]

(1) Watau Alqur’ani mai girma.
(2) Watau a zamanin Manzon Allah ( ) wanda mushirikan Quraishawa suka gani da idonsu, bayan sun nemi ya nuna musu mu’ujiza.
(3) Shi ne Mala’ika Israfilu ( ) mai busa a qaho.
(4) Watau lokacin fitowa daga qaburbura.

خُشَّعًا أَبۡصَٰرُهُمۡ يَخۡرُجُونَ مِنَ ٱلۡأَجۡدَاثِ كَأَنَّهُمۡ جَرَادٞ مُّنتَشِرٞ ﴿٧﴾
مُّهۡطِعِينَ إِلَى ٱلدَّاعِۖ يَقُولُ ٱلۡكَٰفِرُونَ هَٰذَا يَوۡمٌ عَسِرٞ ﴿٨﴾ كَذَّبَتۡ
قَبۡلَهُمۡ قَوۡمُ نُوحٖ فَكَذَّبُواْ عَبۡدَنَا وَقَالُواْ مَجۡنُونٞ وَٱزۡدُجِرَ ﴿٩﴾ فَدَعَا
رَبَّهُۥٓ أَنِّي مَغۡلُوبٞ فَٱنتَصِرۡ ﴿١٠﴾ فَفَتَحۡنَآ أَبۡوَٰبَ ٱلسَّمَآءِ بِمَآءٖ مُّنۡهَمِرٖ
﴿١١﴾ وَفَجَّرۡنَا ٱلۡأَرۡضَ عُيُونٗا فَٱلۡتَقَى ٱلۡمَآءُ عَلَىٰٓ أَمۡرٖ قَدۡ قُدِرَ ﴿١٢﴾
وَحَمَلۡنَٰهُ عَلَىٰ ذَاتِ أَلۡوَٰحٖ وَدُسُرٖ ﴿١٣﴾ تَجۡرِي بِأَعۡيُنِنَا جَزَآءٗ لِّمَن كَانَ
كُفِرَ ﴿١٤﴾ وَلَقَد تَّرَكۡنَٰهَآ ءَايَةٗ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ﴿١٥﴾ فَكَيۡفَ كَانَ
عَذَابِي وَنُذُرِ ﴿١٦﴾ وَلَقَدۡ يَسَّرۡنَا ٱلۡقُرۡءَانَ لِلذِّكۡرِ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ﴿١٧﴾
كَذَّبَتۡ عَادٞ فَكَيۡفَ كَانَ عَذَابِي وَنُذُرِ ﴿١٨﴾ إِنَّآ أَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمۡ رِيحٗا
صَرۡصَرٗا فِي يَوۡمِ نَحۡسٖ مُّسۡتَمِرّٖ ﴿١٩﴾ تَنزِعُ ٱلنَّاسَ كَأَنَّهُمۡ أَعۡجَازُ نَخۡلٖ
مُّنقَعِرٖ ﴿٢٠﴾ فَكَيۡفَ كَانَ عَذَابِي وَنُذُرِ ﴿٢١﴾ وَلَقَدۡ يَسَّرۡنَا ٱلۡقُرۡءَانَ
لِلذِّكۡرِ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ﴿٢٢﴾ كَذَّبَتۡ ثَمُودُ بِٱلنُّذُرِ ﴿٢٣﴾ فَقَالُوٓاْ أَبَشَرٗا
مِّنَّا وَٰحِدٗا نَّتَّبِعُهُۥٓ إِنَّآ إِذٗا لَّفِي ضَلَٰلٖ وَسُعُرٍ ﴿٢٤﴾ أَءُلۡقِيَ ٱلذِّكۡرُ عَلَيۡهِ
مِنۢ بَيۡنِنَا بَلۡ هُوَ كَذَّابٌ أَشِرٞ ﴿٢٥﴾ سَيَعۡلَمُونَ غَدٗا مَّنِ ٱلۡكَذَّابُ ٱلۡأَشِرُ
﴿٢٦﴾ إِنَّا مُرۡسِلُواْ ٱلنَّاقَةِ فِتۡنَةٗ لَّهُمۡ فَٱرۡتَقِبۡهُمۡ وَٱصۡطَبِرۡ ﴿٢٧﴾

(7) Idanuwansu suna a ƙasƙance suna fitowa daga ƙaburbura, kai ka ce su farin ɗango ne masu bazuwa
(8) Suna gaggawa zuwa ga mai kiran; kafirai za su rika cewa: "Wannan rana ce mai tsanani."
(9) Mutanen Nuhu sun ƙaryata kafin su (Kuraishawa), sai suka ƙaryata Bawanmu suka kuma ce, mahaukaci ne, aka kuma kyare (shi)
(10) Sai ya roƙi Ubangijinsa (cewa): "Lalle an fi ƙarfina, sai Ka taimaka."
(11) Sai Muka buɗe ƙofofin sama da ruwa mai kwararowa
(12) Muka kuma ɓuɓɓugar da idanuwan ruwa daga ƙasa, sai ruwayen suka haɗu a bisa al'amarin da aka riga aka ƙaddara
(13) Muka kuma ɗauke shi a kan (jirgin ruwa) mai alluna da ƙusoshi
(14) Yana gudu a kan idonmu, don ya zama sakayya ga wanda aka kafirce wa (watau Nuhu)
(15) Haƙiƙa kuma Mun bar (abin da ya faru) ya zama aya, to ko akwai mai wa'azantuwa?
(16) To ƙaƙa azabata da gargaɗina suka kasance?
(17) Haƙiƙa kuma Mun sauƙaƙe Alƙur'ani don tunasarwa da hadda, to ko akwai mai wa'azantuwa?
(18) Adawa sun ƙaryata (Annabinsu), to ƙaƙa azabata da gargaɗina suka kasance?
(19) Lalle Mu Mun aiko musu da iska mai ƙarfi a ranar shu'umci mai zarcewa
(20) Tana tumɓuke mutane[1] ta kayar su, kai ka ce su kututturan dabinai ne da aka tuttunɓuke
(21) To ƙaƙa azabata da gargaɗina suka kasance?
(22) Kuma haƙiƙa Mun sauƙaƙe Alƙur'ani don tunatarwa, to ko akwai mai wa'azantuwa?
(23) Samudawa sun ƙaryata gargaɗi
(24) Sannan suka ce: "Yanzu mutum ɗaya daga cikinmu ne za mu bi? To lalle idan mun yi haka, mun tabbata cikin ɓata da hauka
(25) "Yanzu (zai yiwu) a saukar masa da wahayi a tsakaninmu? A'a, shi dai maƙaryaci ne mai tsananin girman kai."
(26) A gobe lalle za su san wane ne maƙaryacin mai girman kai
(27) Lalle Mu Masu aiko taguwa ne don ta zama fitina a gare su, saboda haka ka saurara musu, kuma ka jure

(1) Watau daga doron qasa ta yi sama da su sannan ta kifo da su ta kawunansu su faxo qasa a mace.

وَنَبِّئْهُمْ أَنَّ ٱلْمَآءَ قِسْمَةٌۢ بَيْنَهُمْ ۖ كُلُّ شِرْبٍ مُّحْتَضَرٌ ﴿٢٨﴾ فَنَادَوْا۟ صَاحِبَهُمْ
فَتَعَاطَىٰ فَعَقَرَ ﴿٢٩﴾ فَكَيْفَ كَانَ عَذَابِى وَنُذُرِ ﴿٣٠﴾ إِنَّآ أَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ
صَيْحَةً وَٰحِدَةً فَكَانُوا۟ كَهَشِيمِ ٱلْمُحْتَظِرِ ﴿٣١﴾ وَلَقَدْ يَسَّرْنَا ٱلْقُرْءَانَ
لِلذِّكْرِ فَهَلْ مِن مُّدَّكِرٍ ﴿٣٢﴾ كَذَّبَتْ قَوْمُ لُوطٍۭ بِٱلنُّذُرِ ﴿٣٣﴾ إِنَّآ أَرْسَلْنَا
عَلَيْهِمْ حَاصِبًا إِلَّآ ءَالَ لُوطٍ ۖ نَّجَّيْنَٰهُم بِسَحَرٍ ﴿٣٤﴾ نِّعْمَةً مِّنْ عِندِنَا ۚ
كَذَٰلِكَ نَجْزِى مَن شَكَرَ ﴿٣٥﴾ وَلَقَدْ أَنذَرَهُم بَطْشَتَنَا فَتَمَارَوْا۟ بِٱلنُّذُرِ
﴿٣٦﴾ وَلَقَدْ رَٰوَدُوهُ عَن ضَيْفِهِۦ فَطَمَسْنَآ أَعْيُنَهُمْ فَذُوقُوا۟ عَذَابِى
وَنُذُرِ ﴿٣٧﴾ وَلَقَدْ صَبَّحَهُم بُكْرَةً عَذَابٌ مُّسْتَقِرٌّ ﴿٣٨﴾ فَذُوقُوا۟
عَذَابِى وَنُذُرِ ﴿٣٩﴾ وَلَقَدْ يَسَّرْنَا ٱلْقُرْءَانَ لِلذِّكْرِ فَهَلْ مِن مُّدَّكِرٍ ﴿٤٠﴾
وَلَقَدْ جَآءَ ءَالَ فِرْعَوْنَ ٱلنُّذُرُ ﴿٤١﴾ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا كُلِّهَا فَأَخَذْنَٰهُمْ
أَخْذَ عَزِيزٍ مُّقْتَدِرٍ ﴿٤٢﴾ أَكُفَّارُكُمْ خَيْرٌ مِّنْ أُو۟لَٰٓئِكُمْ أَمْ لَكُم بَرَآءَةٌ
فِى ٱلزُّبُرِ ﴿٤٣﴾ أَمْ يَقُولُونَ نَحْنُ جَمِيعٌ مُّنتَصِرٌ ﴿٤٤﴾ سَيُهْزَمُ ٱلْجَمْعُ
وَيُوَلُّونَ ٱلدُّبُرَ ﴿٤٥﴾ بَلِ ٱلسَّاعَةُ مَوْعِدُهُمْ وَٱلسَّاعَةُ أَدْهَىٰ وَأَمَرُّ ﴿٤٦﴾
إِنَّ ٱلْمُجْرِمِينَ فِى ضَلَٰلٍ وَسُعُرٍ ﴿٤٧﴾ يَوْمَ يُسْحَبُونَ فِى ٱلنَّارِ عَلَىٰ
وُجُوهِهِمْ ذُوقُوا۟ مَسَّ سَقَرَ ﴿٤٨﴾ إِنَّا كُلَّ شَىْءٍ خَلَقْنَٰهُ بِقَدَرٍ ﴿٤٩﴾

(28) Kuma ka ba su labarin cewa ruwan sha an raba ne tsakaninsu (da ita taguwar); kowane akwai ranar shansa
(29) Sai suka kirawo (shaƙiyin) abokin nasu sai ya ɗauki (abin sara) sai ya sare ta
(30) To ƙaƙa azabata da gargaɗina suka kasance?
(31) Lalle Mun aika musu da tsawa guda ɗaya, sai suka zamo kamar duddugar ciyawa a garken makiyayi
(32) Haƙiƙa kuma Mun sauƙaƙe Alƙur'ani don tunatarwa, to ko akwai mai wa'azantuwa?
(33) Mutanen Luɗu sun ƙaryata gargaɗi
(34) Lalle Mun aika musu da iska cike da duwatsu (ta hallaka su), sai dai iyalin Luɗu kaɗai Muka tserar da su a lokacin asuba
(35) (Wannan) ni'ima ce daga wurinmu. Kamar haka Muke saka wa wanda ya yi godiya
(36) Kuma haƙiƙa ya tsoratar da su irin damƙarmu, sai suka yi jayayya da gargaɗin (da ya yi musu)
(37) Haƙiƙa kuma sun nemi baƙinsa[1] da lalata, sai Muka shafe idanuwansu, (Muka ce da su): "Sai ku ɗanɗani azabata da gargaɗina.
(38) Haƙiƙa kuma azaba matabbaciya ta yi musu sammako da asuba.
(39) Saboda haka ku ɗanɗani azabata da gargaɗina."
(40) Haƙiƙa kuma Mun sauƙaƙe Alƙur'ani don tunatarwa, to ko akwai mai wa'azantuwa?
(41) Kuma haƙiƙa gargaɗi ya zo wa mutanen Fir'auna
(42) Suka ƙaryata ayoyinmu dukkaninsu, sai Muka kama su irin kamu na Mabuwayi, Mai iko
(43) Yanzu kafiranku (ku mutanen Makka) su ne suka fi waɗancan alheri, ko kuwa kuna da wata hanya ta kuɓuta ne a cikin littattafan da aka saukar?
(44) A'a, suna dai cewa ne: "Mu jama'a ce wadda za ta ci nasara."
(45) To ba da daɗewa ba za a karya jama'ar tasu[2], su kuma su ba da baya
(46) A'a, alƙiyama ita ce lokacin yi musu azaba, alƙiyama kuwa ita ta fi bala'i, ta kuma fi ɗaci
(47) Lalle masu manyan laifuka suna cikin ɓata da azabar wuta
(48) Ranar da za a ja su cikin wuta a kan fuskokinsu (a ce da su): "Ku ɗanɗani azabar wutar Saƙara."

(1) Su ne mala'iku da suka zo masa a siffar mutane matasa kyawawa.
(2) Haka kuwa ya faru a yaqin Badar lokacin da aka karya lagon kafiran Makka, aka kashe manyansu da dama.

وَمَآ أَمۡرُنَآ إِلَّا وَٰحِدَةٞ كَلَمۡحِۭ بِٱلۡبَصَرِ ٥٠ وَلَقَدۡ أَهۡلَكۡنَآ
أَشۡيَاعَكُمۡ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ٥١ وَكُلُّ شَيۡءٖ فَعَلُوهُ فِي ٱلزُّبُرِ
٥٢ وَكُلُّ صَغِيرٖ وَكَبِيرٖ مُّسۡتَطَرٞ ٥٣ إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ
فِي جَنَّٰتٖ وَنَهَرٖ ٥٤ فِي مَقۡعَدِ صِدۡقٍ عِندَ مَلِيكٖ مُّقۡتَدِرِۢ ٥٥

سُورَةُ الرَّحۡمَٰنِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلرَّحۡمَٰنُ ١ عَلَّمَ ٱلۡقُرۡءَانَ ٢ خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ ٣ عَلَّمَهُ ٱلۡبَيَانَ ٤
ٱلشَّمۡسُ وَٱلۡقَمَرُ بِحُسۡبَانٖ ٥ وَٱلنَّجۡمُ وَٱلشَّجَرُ يَسۡجُدَانِ ٦
وَٱلسَّمَآءَ رَفَعَهَا وَوَضَعَ ٱلۡمِيزَانَ ٧ أَلَّا تَطۡغَوۡاْ فِي ٱلۡمِيزَانِ ٨
وَأَقِيمُواْ ٱلۡوَزۡنَ بِٱلۡقِسۡطِ وَلَا تُخۡسِرُواْ ٱلۡمِيزَانَ ٩ وَٱلۡأَرۡضَ
وَضَعَهَا لِلۡأَنَامِ ١٠ فِيهَا فَٰكِهَةٞ وَٱلنَّخۡلُ ذَاتُ ٱلۡأَكۡمَامِ ١١
وَٱلۡحَبُّ ذُو ٱلۡعَصۡفِ وَٱلرَّيۡحَانُ ١٢ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
١٣ خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ مِن صَلۡصَٰلٖ كَٱلۡفَخَّارِ ١٤ وَخَلَقَ ٱلۡجَآنَّ مِن
مَّارِجٖ مِّن نَّارٖ ١٥ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ١٦ رَبُّ
ٱلۡمَشۡرِقَيۡنِ وَرَبُّ ٱلۡمَغۡرِبَيۡنِ ١٧ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ١٨

(50) Kuma al’amarinmu bai zamanto ba face kalma ɗaya kamar ƙiftawar ido
(51) Haƙiƙa kuma Mun hallakar da ire-irenku[1], to ko akwai mai wa’azantuwa?
(52) Kuma kowane abu da suka aikata yana cikin littattafai
(53) Kowane ƙaramin abu da babba kuma suna nan a rubuce
(54) Lalle masu taƙawa suna cikin gidajen Aljanna da ƙoramu
(55) A mazauni na gaskiya a wurin Mai mulki, Mai iko

Sura Rahman

(1) (Allah) Mai rahama
(2) Shi Ya koyar da Alƙur’ani
(3) Ya halicci mutum
(4) Ya koyar da shi bayani
(5) Rana da wata (suna tafiya) a tsare
(6) Tsirrai da bishiyoyi suna yin sujjada[2]
(7) Sama kuma Ya ɗaga ta, Ya kuma kafa adalci
(8) Don kada ku yi zalunci a abin awo
(9) Kuma ku tabbatar da awo da adalci kada kuma ku tauye abin awo
(10) Kasa kuma Ya yi ta saboda talikai
(11) A cikinta akwai abin marmari da dabinai ma’abota kwasfa
(12) Da ƙwayoyi ma’abota ƙaiƙayi da kuma ganyaye masu ƙanshi
(13) To da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(14) Ya halicci mutum daga busasshen taɓo kamar kasko
(15) Ya kuma halicci aljani daga harshen wuta
(16) Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(17) Ubangijin mahudar rana biyu da mafaɗarta biyu[3]
(18) Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

(1) Watau kafirai irinsu masu taurin kai.
(2) Watau tsirrai waxanda ba sa tashi tsaye da bishiyoyi masu tsayawa a kan sandunansu.
(3) Watau a lokacin sanyi da kuma lokacin zafi.

مَرَجَ ٱلْبَحْرَيْنِ يَلْتَقِيَانِ ﴿١٩﴾ بَيْنَهُمَا بَرْزَخٌ لَّا يَبْغِيَانِ ﴿٢٠﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ
رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٢١﴾ يَخْرُجُ مِنْهُمَا ٱللُّؤْلُؤُ وَٱلْمَرْجَانُ ﴿٢٢﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ
رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٢٣﴾ وَلَهُ ٱلْجَوَارِ ٱلْمُنشَـَٔاتُ فِى ٱلْبَحْرِ كَٱلْأَعْلَـٰمِ ﴿٢٤﴾
فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٢٥﴾ كُلُّ مَنْ عَلَيْهَا فَانٍ ﴿٢٦﴾ وَيَبْقَىٰ وَجْهُ
رَبِّكَ ذُو ٱلْجَلَـٰلِ وَٱلْإِكْرَامِ ﴿٢٧﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٢٨﴾
يَسْـَٔلُهُۥ مَن فِى ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ كُلَّ يَوْمٍ هُوَ فِى شَأْنٍ ﴿٢٩﴾ فَبِأَيِّ
ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٣٠﴾ سَنَفْرُغُ لَكُمْ أَيُّهَ ٱلثَّقَلَانِ ﴿٣١﴾ فَبِأَيِّ
ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٣٢﴾ يَـٰمَعْشَرَ ٱلْجِنِّ وَٱلْإِنسِ إِنِ ٱسْتَطَعْتُمْ
أَن تَنفُذُوا۟ مِنْ أَقْطَارِ ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ فَٱنفُذُوا۟ ۚ لَا تَنفُذُونَ
إِلَّا بِسُلْطَـٰنٍ ﴿٣٣﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٣٤﴾ يُرْسَلُ عَلَيْكُمَا
شُوَاظٌ مِّن نَّارٍ وَنُحَاسٌ فَلَا تَنتَصِرَانِ ﴿٣٥﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ﴿٣٦﴾ فَإِذَا ٱنشَقَّتِ ٱلسَّمَآءُ فَكَانَتْ وَرْدَةً كَٱلدِّهَانِ
﴿٣٧﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٣٨﴾ فَيَوْمَئِذٍ لَّا يُسْـَٔلُ عَن
ذَنۢبِهِۦٓ إِنسٌ وَلَا جَآنٌّ ﴿٣٩﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٤٠﴾
يُعْرَفُ ٱلْمُجْرِمُونَ بِسِيمَـٰهُمْ فَيُؤْخَذُ بِٱلنَّوَٰصِى وَٱلْأَقْدَامِ ﴿٤١﴾

(19) Ya gudanar da koguna guda biyu suna haɗuwa (da juna)
(20) A tsakaninsu (kuma) akwai wani shamaki da ya hana su shiga juna
(21) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(22) Lu'ulu'u da murjani suna fita daga cikinsu
(23) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(24) Jiragen ruwa kuma da aka yi su suna gudu a cikin kogi kamar manya-manyan duwatsu nasa ne
(25) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (26) Dukkan wanda yake kanta (ƙasar) ƙararre ne (27) Fuskar Ubangijinka kuwa Ma'abocin girma da karamci ne kawai take wanzuwa (28) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(29) Duk wanda yake cikin sammai da ƙasa yana roƙon Sa. Kowane lokacin Shi a cikin wani sha'ani yake (30) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (31) Ba da daɗewa ba za Mu dawo kanku ya ku mutane da aljannu (32) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(33) Ya ku jama'ar aljannu da mutane, idan kun sami ikon ficewa daga cikin sassan sammai da ƙasa to ku fice. Ba za ku fice ba sai da samun wani ƙarfi[1] (34) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (35) Za a aiko muku (ku mutane da aljannu) da balbalin wuta da kuma hayaƙi, saboda haka ba za ku iya kare kanku (daga gare shi) ba (36) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (37) Sannan idan sama ta kekkece ta zama jajir kamar jar fata[2] (38) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (39) Sannan a wannan rana ba a tambayar mutum ko aljan laifinsa (40) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (41) Ana gane manyan masu laifi da alamominsu[3], sai a kama su ta makwarkwaɗa da dugadugai

(1) Watau ba za su kuvuce wa Allah ba sai idan suna da wata hujja ko wani qarfi, wanda kuma su ma sun tabbata ba su da shi.
(2) Watau saboda an gusar da hasken taurarin cikinta gaba xaya.
(3) Saboda fuskokinsu za su yi baqi qirin, idanuwansu kuma za su yi jawur.

فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٤٢﴾ هَٰذِهِۦ جَهَنَّمُ ٱلَّتِى يُكَذِّبُ بِهَا
ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿٤٣﴾ يَطُوفُونَ بَيْنَهَا وَبَيْنَ حَمِيمٍ ءَانٍ ﴿٤٤﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ
رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٤٥﴾ وَلِمَنْ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ جَنَّتَانِ ﴿٤٦﴾ فَبِأَيِّ
ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٤٧﴾ ذَوَاتَآ أَفْنَانٍ ﴿٤٨﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ﴿٤٩﴾ فِيهِمَا عَيْنَانِ تَجْرِيَانِ ﴿٥٠﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
﴿٥١﴾ فِيهِمَا مِن كُلِّ فَٰكِهَةٍ زَوْجَانِ ﴿٥٢﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
﴿٥٣﴾ مُتَّكِـِٔينَ عَلَىٰ فُرُشٍۭ بَطَآئِنُهَا مِنْ إِسْتَبْرَقٍ ۚ وَجَنَى ٱلْجَنَّتَيْنِ دَانٍ
﴿٥٤﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٥٥﴾ فِيهِنَّ قَٰصِرَٰتُ ٱلطَّرْفِ
لَمْ يَطْمِثْهُنَّ إِنسٌ قَبْلَهُمْ وَلَا جَآنٌّ ﴿٥٦﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
﴿٥٧﴾ كَأَنَّهُنَّ ٱلْيَاقُوتُ وَٱلْمَرْجَانُ ﴿٥٨﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
﴿٥٩﴾ هَلْ جَزَآءُ ٱلْإِحْسَٰنِ إِلَّا ٱلْإِحْسَٰنُ ﴿٦٠﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ﴿٦١﴾ وَمِن دُونِهِمَا جَنَّتَانِ ﴿٦٢﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ﴿٦٣﴾ مُدْهَآمَّتَانِ ﴿٦٤﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
﴿٦٥﴾ فِيهِمَا عَيْنَانِ نَضَّاخَتَانِ ﴿٦٦﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٦٧﴾
فِيهِمَا فَٰكِهَةٌ وَنَخْلٌ وَرُمَّانٌ ﴿٦٨﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٦٩﴾

(42) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(43) (Za a ce da su): Wannan ita ce Jahannamar da manyan masu laifi suke ƙaryatawa
(44) Za su riƙa kai-kawo tsakaninta da tafasasshen ruwa mai tsananin zafi
(45) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(46) Duk wanda kuwa ya ji tsoron tsayuwa (gaban) Ubangijinsa yana da Aljanna biyu
(47) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(48) Ma'abota rassan bishiyoyi
**(49) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (50) A cikinsu akwai idanuwa (na ruwa) guda biyu masu gudana (51) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (52) A cikinsu akwai (dangi) biyu na kowane abin marmari (53) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (54) Suna kishingiɗe a kan shimfiɗu da shafin cikinsu na kakkauran alhariri ne. Kuma 'ya'yan bishiyoyin Aljannatai biyun kusa suke (da kowa) (55) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (56) A cikinsu akwai (mata) masu taƙaita kallo (ga mazajensu, waɗanda) wani mutum ko aljan bai taɓa shafar su ba a gabaninsu (57) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (58) Kai ka ce su yaƙutu ne da murjani (59) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (60) Shin akwai wani sakamako na kyautatawa in ba kyautatawa ba? (61) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (62) A ƙasa da su kuma akwai wasu aljannatai guda biyu (63) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (64) Masu tsananin kore (65) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (66) A cikinsu (kuma) akwai idanuwan (ruwa) guda biyu masu feshi (67) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa? (68) A cikinsu (kuma) akwai abin marmari da dabino da ruman (69) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

فِيهِنَّ خَيْرَٰتٌ حِسَانٌ ﴿٧٠﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
﴿٧١﴾ حُورٌ مَّقْصُورَٰتٌ فِى ٱلْخِيَامِ ﴿٧٢﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ﴿٧٣﴾ لَمْ يَطْمِثْهُنَّ إِنسٌ قَبْلَهُمْ وَلَا جَآنٌّ ﴿٧٤﴾ فَبِأَيِّ
ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٧٥﴾ مُتَّكِـِٔينَ عَلَىٰ رَفْرَفٍ خُضْرٍ
وَعَبْقَرِىٍّ حِسَانٍ ﴿٧٦﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٧٧﴾
تَبَارَكَ ٱسْمُ رَبِّكَ ذِى ٱلْجَلَٰلِ وَٱلْإِكْرَامِ ﴿٧٨﴾

سُورَةُ الْوَاقِعَةِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِذَا وَقَعَتِ ٱلْوَاقِعَةُ ﴿١﴾ لَيْسَ لِوَقْعَتِهَا كَاذِبَةٌ ﴿٢﴾ خَافِضَةٌ رَّافِعَةٌ
﴿٣﴾ إِذَا رُجَّتِ ٱلْأَرْضُ رَجًّا ﴿٤﴾ وَبُسَّتِ ٱلْجِبَالُ بَسًّا ﴿٥﴾ فَكَانَتْ
هَبَآءً مُّنۢبَثًّا ﴿٦﴾ وَكُنتُمْ أَزْوَٰجًا ثَلَٰثَةً ﴿٧﴾ فَأَصْحَٰبُ ٱلْمَيْمَنَةِ
مَآ أَصْحَٰبُ ٱلْمَيْمَنَةِ ﴿٨﴾ وَأَصْحَٰبُ ٱلْمَشْـَٔمَةِ مَآ أَصْحَٰبُ
ٱلْمَشْـَٔمَةِ ﴿٩﴾ وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلسَّٰبِقُونَ ﴿١٠﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلْمُقَرَّبُونَ ﴿١١﴾
فِى جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ﴿١٢﴾ ثُلَّةٌ مِّنَ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿١٣﴾ وَقَلِيلٌ مِّنَ ٱلْـَٔاخِرِينَ
﴿١٤﴾ عَلَىٰ سُرُرٍ مَّوْضُونَةٍ ﴿١٥﴾ مُّتَّكِـِٔينَ عَلَيْهَا مُتَقَٰبِلِينَ ﴿١٦﴾

(70) A cikinsu (watau gidajen Aljannar) akwai mata nagartattu kyawawa
(71) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(72) (Matayen) masu fari da baƙin ido ne, suna kawwame cikin tantuna
(73) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(74) Wani mutum ko aljan bai taɓa shafar su ba a gabaninsu
(75) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(76) Suna kishingiɗe a kan matasan kai koraye, da kuma kilisai kyawawa
(77) Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?
(78) Albarkatun sunan Ubangijinka Ma'abocin girma da ɗaukaka sun yawaita

Sura Waƙi'a

(1) [1]Idan mai afkowa ta afku (watau alƙiyama)
(2) Babu wani (rai) mai ƙaryata aukuwarta
(3) Degradante (para alguns) e eɗaltador (para outros)
(4) Idan aka girgiza ƙasa girgizawa
(5) Aka kuma dandaƙe duwatsu dandaƙewa
(6) Suka zama ƙura abar sheƙewa
(7) Kuka kuma kasance dangogi guda uku
(8) To ma'abota dama fa, mamakin darajar ma'abota dama!
(9) Da kuma ma'abota hagu, mamakin wulaƙantar ma'abota hagu!
(10) Da kuma masu rige-rige (zuwa alheri)
(11) Waɗannan su ne makusanta
(12) A cikin gidajen Aljanna na ni'ima
(13) Su jama'a ne (masu yawa) daga (al'ummun) farko
(14) Kuma kaɗan ne daga (al'ummun) ƙarshe
(15) Suna kan gadaje masu adon zinari
(16) Suna kishingiɗe a kansu suna fuskantar juna

يَطُوفُ عَلَيْهِمْ وِلْدَٰنٌ مُّخَلَّدُونَ ﴿١٧﴾ بِأَكْوَابٍ وَأَبَارِيقَ وَكَأْسٍ مِّن مَّعِينٍ
﴿١٨﴾ لَّا يُصَدَّعُونَ عَنْهَا وَلَا يُنزِفُونَ ﴿١٩﴾ وَفَٰكِهَةٍ مِّمَّا يَتَخَيَّرُونَ
﴿٢٠﴾ وَلَحْمِ طَيْرٍ مِّمَّا يَشْتَهُونَ ﴿٢١﴾ وَحُورٌ عِينٌ ﴿٢٢﴾ كَأَمْثَٰلِ ٱللُّؤْلُوِ
ٱلْمَكْنُونِ ﴿٢٣﴾ جَزَآءًۢ بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٢٤﴾ لَا يَسْمَعُونَ فِيهَا لَغْوًا
وَلَا تَأْثِيمًا ﴿٢٥﴾ إِلَّا قِيلًا سَلَٰمًا سَلَٰمًا ﴿٢٦﴾ وَأَصْحَٰبُ ٱلْيَمِينِ مَآ أَصْحَٰبُ
ٱلْيَمِينِ ﴿٢٧﴾ فِى سِدْرٍ مَّخْضُودٍ ﴿٢٨﴾ وَطَلْحٍ مَّنضُودٍ ﴿٢٩﴾ وَظِلٍّ مَّمْدُودٍ
﴿٣٠﴾ وَمَآءٍ مَّسْكُوبٍ ﴿٣١﴾ وَفَٰكِهَةٍ كَثِيرَةٍ ﴿٣٢﴾ لَّا مَقْطُوعَةٍ وَلَا مَمْنُوعَةٍ
﴿٣٣﴾ وَفُرُشٍ مَّرْفُوعَةٍ ﴿٣٤﴾ إِنَّآ أَنشَأْنَٰهُنَّ إِنشَآءً ﴿٣٥﴾ فَجَعَلْنَٰهُنَّ أَبْكَارًا
﴿٣٦﴾ عُرُبًا أَتْرَابًا ﴿٣٧﴾ لِّأَصْحَٰبِ ٱلْيَمِينِ ﴿٣٨﴾ ثُلَّةٌ مِّنَ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٣٩﴾
وَثُلَّةٌ مِّنَ ٱلْءَاخِرِينَ ﴿٤٠﴾ وَأَصْحَٰبُ ٱلشِّمَالِ مَآ أَصْحَٰبُ ٱلشِّمَالِ
﴿٤١﴾ فِى سَمُومٍ وَحَمِيمٍ ﴿٤٢﴾ وَظِلٍّ مِّن يَحْمُومٍ ﴿٤٣﴾ لَّا بَارِدٍ
وَلَا كَرِيمٍ ﴿٤٤﴾ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ قَبْلَ ذَٰلِكَ مُتْرَفِينَ ﴿٤٥﴾ وَكَانُوا۟
يُصِرُّونَ عَلَى ٱلْحِنثِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٤٦﴾ وَكَانُوا۟ يَقُولُونَ أَئِذَا مِتْنَا وَكُنَّا
تُرَابًا وَعِظَٰمًا أَءِنَّا لَمَبْعُوثُونَ ﴿٤٧﴾ أَوَءَابَآؤُنَا ٱلْأَوَّلُونَ ﴿٤٨﴾ قُلْ إِنَّ
ٱلْأَوَّلِينَ وَٱلْءَاخِرِينَ ﴿٤٩﴾ لَمَجْمُوعُونَ إِلَىٰ مِيقَٰتِ يَوْمٍ مَّعْلُومٍ ﴿٥٠﴾

(17) Yara samari dawwamammu (masu hidima) za su rika zagaya su
(18) Da kofuna (marasa marikai) da butoci masu hannaye da kuma kokuna na giya
(19) Ba sa ciwon kai saboda ita, kuma ba sa buguwa
(20) Da kuma ababan marmari na abin da suke so su zaba
(21) Da kuma naman tsuntsaye na abin da suke sha'awa
(22) Da kuma matan Hurul-Ini
(23) Kamar misalin lu'ulu'u da yake cikin kwasfa
(24) Sakamako ne na abin da suka kasance suna aikatawa
(25)Ba sa kuma jin wani zancen banza da mai sa zunubi a cikinta (26) Sai dai fadar salamun-salamun[1] (27) Ma'abota hannun dama kuwa, mamakin darajar ma'abota hannun dama! (28) Suna cikin 'ya'yan itacen magarya marasa kaya (29) Da kuma ayaba mai 'ya'ya daba-daba (30) Da inuwa madawwamiya (31) Da kuma ruwa mai kwarara (32) Da ababen marmari masu yawa (33) Ba masu yankewa ba kuma ba ababen hanawa ba (34) Da shimfidu masu daraja (35) Lalle Mu ne Muka kage su ('yan matan Aljanna) sabuwar kagowa (36) Sannan Muka sanya su budurwai
(37) Masu begen mazajensu, tsarekun juna (38) Don ma'abota hannun dama (39) Su jama'a ne (masu yawa) daga (al'ummun) farko (40) Kuma jama'a ne (masu yawa) daga (al'ummar) karshe (41) Ma'abota hannun hagu kuma, mamakin kaskancin ma'abota hannun hagu! (42) Suna cikin iska mai tsananin zafi da kuma tafasasshen ruwa (43) Da kuma inuwa ta turnukun hayaki (44) Ba mai sanyi ba, kuma ba mai daraja ba (45) Lalle su sun kasance masu holewa ne kafin wannan (46) Sun kuma kasance suna dogewa a kan zunubi mai girma.[2] (47) Sun kuma kasance suna cewa: "Yanzu idan mun mutu, mun zama kasa da kasusuwa, yanzu lalle za a tashe mu? (48) "Hakanan ma iyayenmu na farko?" (49) Ka ce: "Lalle na farkon da na karshen (50) "Tabbas za a tattara su zuwa wani lokaci na rana sananniya

(1) Watau sallamar mala'iku a gare su da wadda za su riqa yi wa junansu.

(2) Watau babban laifi na kafirci da bautar wanin Allah.

ثُمَّ إِنَّكُمْ أَيُّهَا ٱلضَّآلُّونَ ٱلْمُكَذِّبُونَ ﴿٥١﴾ لَآكِلُونَ مِن شَجَرٍ مِّن زَقُّومٍ ﴿٥٢﴾
فَمَالِـُٔونَ مِنْهَا ٱلْبُطُونَ ﴿٥٣﴾ فَشَٰرِبُونَ عَلَيْهِ مِنَ ٱلْحَمِيمِ ﴿٥٤﴾ فَشَٰرِبُونَ
شُرْبَ ٱلْهِيمِ ﴿٥٥﴾ هَٰذَا نُزُلُهُمْ يَوْمَ ٱلدِّينِ ﴿٥٦﴾ نَحْنُ خَلَقْنَٰكُمْ فَلَوْلَا
تُصَدِّقُونَ ﴿٥٧﴾ أَفَرَءَيْتُم مَّا تُمْنُونَ ﴿٥٨﴾ ءَأَنتُمْ تَخْلُقُونَهُۥٓ أَمْ نَحْنُ
ٱلْخَٰلِقُونَ ﴿٥٩﴾ نَحْنُ قَدَّرْنَا بَيْنَكُمُ ٱلْمَوْتَ وَمَا نَحْنُ بِمَسْبُوقِينَ ﴿٦٠﴾
عَلَىٰٓ أَن نُّبَدِّلَ أَمْثَٰلَكُمْ وَنُنشِئَكُمْ فِى مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿٦١﴾ وَلَقَدْ
عَلِمْتُمُ ٱلنَّشْأَةَ ٱلْأُولَىٰ فَلَوْلَا تَذَكَّرُونَ ﴿٦٢﴾ أَفَرَءَيْتُم مَّا تَحْرُثُونَ
﴿٦٣﴾ ءَأَنتُمْ تَزْرَعُونَهُۥٓ أَمْ نَحْنُ ٱلزَّٰرِعُونَ ﴿٦٤﴾ لَوْ نَشَآءُ لَجَعَلْنَٰهُ
حُطَٰمًا فَظَلْتُمْ تَفَكَّهُونَ ﴿٦٥﴾ إِنَّا لَمُغْرَمُونَ ﴿٦٦﴾ بَلْ نَحْنُ
مَحْرُومُونَ ﴿٦٧﴾ أَفَرَءَيْتُمُ ٱلْمَآءَ ٱلَّذِى تَشْرَبُونَ ﴿٦٨﴾ ءَأَنتُمْ أَنزَلْتُمُوهُ
مِنَ ٱلْمُزْنِ أَمْ نَحْنُ ٱلْمُنزِلُونَ ﴿٦٩﴾ لَوْ نَشَآءُ جَعَلْنَٰهُ أُجَاجًا فَلَوْلَا
تَشْكُرُونَ ﴿٧٠﴾ أَفَرَءَيْتُمُ ٱلنَّارَ ٱلَّتِى تُورُونَ ﴿٧١﴾ ءَأَنتُمْ أَنشَأْتُمْ
شَجَرَتَهَآ أَمْ نَحْنُ ٱلْمُنشِـُٔونَ ﴿٧٢﴾ نَحْنُ جَعَلْنَٰهَا تَذْكِرَةً وَمَتَٰعًا
لِّلْمُقْوِينَ ﴿٧٣﴾ فَسَبِّحْ بِٱسْمِ رَبِّكَ ٱلْعَظِيمِ ﴿٧٤﴾ * فَلَآ أُقْسِمُ
بِمَوَٰقِعِ ٱلنُّجُومِ ﴿٧٥﴾ وَإِنَّهُۥ لَقَسَمٌ لَّوْ تَعْلَمُونَ عَظِيمٌ ﴿٧٦﴾

(51) "Sannan lalle ku kuma wadannan batattu masu karyatawa
(52) "Tabbas za ku ci daga bishiyar Zakkumu(1)
(53) "Sannan za ku cika cikunanku da ita
(54) "Sannan za ku sha tafasasshen ruwa a kanta
(55) "Sannan za ku sha irin shan rakuma masu jin kishirwa."
(56) Wannan ita ce gararsu a ranar sakamako
(57) Mu ne Muka halicce ku, me ya sa ba kwa gaskatawa?
(58) Ba kwa ganin maniyyi da kuke zubawa
(59) Shin ku ne kuke halittar sa, ko kuwa Mu ne Masu halittar?
(60) Mu ne Muke kaddara mutuwa a tsakaninku, kuma Mu ba Masu gajiyawa ba ne
(61) A kan Mu musanya irinku Mu kuma halitta ku cikin abin da ba ku sani ba
(62) Hakika kuma ku kun san halitta ta farko, don me ba kwa wa'azantuwa?
(63) Ku ba Ni labarin abin da kuke nomawa?
(64) Shin ku ne kuke tsiro da shi, ko Mu ne Masu tsirarwar?
(65) Idan da Mun ga dama tabbas da Mun mayar da shi karmami, sai ku wayi gari kuna mamaki
(66) (Kuna cewa): "Lalle mu an dora mana asara."
(67) "A'a, mu dai an hana mu ne."
(68) Ku ba Ni labarin ruwa wanda kuke sha
(69) Yanzu ku ne kuke sauko da shi daga girgije, ko kuwa Mu ne masu saukarwar?
(70) Da Mun ga dama da Mun mayar da shi (ruwa) mai zartsi, to don me ba kwa godewa?
(71) Ku ba Ni labarin wutar da kuke kunnawa
(72) Yanzu ku ne kuka halicci bishiyarta, ko kuwa Mu ne Masu halittar?
(73) Mu ne Muka sanya ta wa'azi da kuma abin amfani ga matafiya
(74) Saboda haka sai ka tsarkake Sunan Ubangijinka Mai girma
(75) To ina yin rantsuwa da mafadar taurari
(76) Lalle ita kuwa rantsuwa ce mai girma, da kuna ganewa.(1)

(1) Watau wata bishiya ce mafi muni da sharri a wutar jahannama.
(2) Domin taurari da tafiyarsu a sararin sama abu ne mai cike da ayoyi da darussa masu ximbin yawa.

إِنَّهُۥ لَقُرْءَانٌ كَرِيمٌ ﴿٧٧﴾ فِى كِتَٰبٍ مَّكْنُونٍ ﴿٧٨﴾ لَّا يَمَسُّهُۥٓ إِلَّا
ٱلْمُطَهَّرُونَ ﴿٧٩﴾ تَنزِيلٌ مِّن رَّبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٨٠﴾ أَفَبِهَٰذَا ٱلْحَدِيثِ
أَنتُم مُّدْهِنُونَ ﴿٨١﴾ وَتَجْعَلُونَ رِزْقَكُمْ أَنَّكُمْ تُكَذِّبُونَ ﴿٨٢﴾ فَلَوْلَآ
إِذَا بَلَغَتِ ٱلْحُلْقُومَ ﴿٨٣﴾ وَأَنتُمْ حِينَئِذٍ تَنظُرُونَ ﴿٨٤﴾ وَنَحْنُ أَقْرَبُ
إِلَيْهِ مِنكُمْ وَلَٰكِن لَّا تُبْصِرُونَ ﴿٨٥﴾ فَلَوْلَآ إِن كُنتُمْ غَيْرَ مَدِينِينَ
﴿٨٦﴾ تَرْجِعُونَهَآ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٨٧﴾ فَأَمَّآ إِن كَانَ مِنَ ٱلْمُقَرَّبِينَ
﴿٨٨﴾ فَرَوْحٌ وَرَيْحَانٌ وَجَنَّتُ نَعِيمٍ ﴿٨٩﴾ وَأَمَّآ إِن كَانَ مِنْ أَصْحَٰبِ
ٱلْيَمِينِ ﴿٩٠﴾ فَسَلَٰمٌ لَّكَ مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلْيَمِينِ ﴿٩١﴾ وَأَمَّآ إِن كَانَ مِنَ
ٱلْمُكَذِّبِينَ ٱلضَّآلِّينَ ﴿٩٢﴾ فَنُزُلٌ مِّنْ حَمِيمٍ ﴿٩٣﴾ وَتَصْلِيَةُ جَحِيمٍ
﴿٩٤﴾ إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ حَقُّ ٱلْيَقِينِ ﴿٩٥﴾ فَسَبِّحْ بِٱسْمِ رَبِّكَ ٱلْعَظِيمِ ﴿٩٦﴾

سُورَةُ الْحَدِيدِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿١﴾ لَهُۥ مُلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ يُحْىِۦ وَيُمِيتُ ۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٢﴾ هُوَ
ٱلْأَوَّلُ وَٱلْءَاخِرُ وَٱلظَّٰهِرُ وَٱلْبَاطِنُ ۖ وَهُوَ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿٣﴾

(77) Lalle shi Alkur'ani ne mai girma
(78) A cikin littafi abin kiyayewa (daga wani sauyi).(1)
(79) Babu mai taba shi sai tsarkakakku
(80) Saukakke ne daga Ubangijin talikai
(81) Yanzu wannan zance kuke karyatawa?
(82) Kuke kuma sanya (godiyar) arzikinku shi ne ku rika karyatawa?
(83) Me ya hana idan (rai) ya isa makogwaro
(84) Ku kuma a lokacin kuna kallo
(85) Mu ne kuwa Muka fi ku kusanci da shi, sai dai kuma ba kwa gani
(86) Me ya hana idan da kun zamanto ba wadanda za a tasa ba ne
(87) Ku dawo da shi (ran) mana idan kun kasance masu gaskiya
(88) Amma kuma idan (mai mutuwar) ya kasance daga makusanta
(89) To (sakamakonsa) hutu ne da arziki mai dadi, da kuma Aljannar ni'ima
(90) Idan kuma ya kasance daga ma'abota hannun dama ne
(91) To aminci ya tabbata a gare ka don zamanka na hannun dama
(92) Idan kuwa ya kasance daga masu karyatawa ne batattu
(93) To kabaki ne na tafasasshen ruwa (sakamakonsa)
(94) Da kuma shiga wutar Jahannama
(95) Lalle wannan (bayani na cikin wannan Surar) shi ne hakikanin gaskiya
(96) To ka yi tasbihi da tsarkake sunan Ubangijinka mai girma

Sura Hadid

(1) Abin da yake cikin sammai da kasa ya yi tasbihi ga Allah; Shi ne kuma Mabuwayi, Mai hikima
(2) Mulkin sammai da kasa nasa ne; Yana rayawa, Yana kuma kashewa; kuma Shi Mai iko ne a kan komai
(3) Shi ne Na farko kuma Na karshe, kuma Bayyananne kuma Boyayye(2); Shi kuma Masanin komai ne

(1) Shi ne Lauhul Mahfuz.
(2) Na farko, watau babu wani abu gabaninsa. Na qarshe, watau babu wani abu bayansa. Bayyananne, watau babu wani abu sama da shi. Voyayye, watau babu wani abu da ya fi shi vuya.

هُوَ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ
عَلَى ٱلْعَرْشِ ۖ يَعْلَمُ مَا يَلِجُ فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا يَخْرُجُ مِنْهَا وَمَا يَنزِلُ مِنَ
ٱلسَّمَآءِ وَمَا يَعْرُجُ فِيهَا ۖ وَهُوَ مَعَكُمْ أَيْنَ مَا كُنتُمْ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ
بَصِيرٌ ﴿٤﴾ لَّهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرْجَعُ ٱلْأُمُورُ
﴿٥﴾ يُولِجُ ٱلَّيْلَ فِى ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِى ٱلَّيْلِ ۚ وَهُوَ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ
ٱلصُّدُورِ ﴿٦﴾ ءَامِنُوا۟ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَأَنفِقُوا۟ مِمَّا جَعَلَكُم
مُّسْتَخْلَفِينَ فِيهِ ۖ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مِنكُمْ وَأَنفَقُوا۟ لَهُمْ أَجْرٌ كَبِيرٌ ﴿٧﴾
وَمَا لَكُمْ لَا تُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلرَّسُولُ يَدْعُوكُمْ لِتُؤْمِنُوا۟ بِرَبِّكُمْ وَقَدْ
أَخَذَ مِيثَٰقَكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٨﴾ هُوَ ٱلَّذِى يُنَزِّلُ عَلَىٰ عَبْدِهِۦٓ
ءَايَٰتٍۭ بَيِّنَٰتٍ لِّيُخْرِجَكُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ ۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ بِكُمْ
لَرَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿٩﴾ وَمَا لَكُمْ أَلَّا تُنفِقُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلِلَّهِ مِيرَٰثُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ لَا يَسْتَوِى مِنكُم مَّنْ أَنفَقَ مِن قَبْلِ ٱلْفَتْحِ
وَقَٰتَلَ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ أَعْظَمُ دَرَجَةً مِّنَ ٱلَّذِينَ أَنفَقُوا۟ مِنۢ بَعْدُ وَقَٰتَلُوا۟ ۚ
وَكُلًّا وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلْحُسْنَىٰ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ﴿١٠﴾ مَّن ذَا
ٱلَّذِى يُقْرِضُ ٱللَّهَ قَرْضًا حَسَنًا فَيُضَٰعِفَهُۥ لَهُۥ وَلَهُۥٓ أَجْرٌ كَرِيمٌ ﴿١١﴾

(4) Shi ne wanda Ya halicci sammai da ƙasa cikin kwana shida, sannan Ya daidaitu a kan Al'arshi. Yana sane da abin da yake shiga cikin ƙasa da abin da yake fitowa daga cikinta, da kuma abin da yake saukowa daga sama da abin da yake hawa cikinta; kuma Shi Yana tare da ku a duk inda kuka kasance[1]. Allah kuwa Mai ganin duk abin da kuke aikatawa ne

(5) Mulkin sammai da ƙasa nasa ne. Kuma ga Allah ake mayar da al'amura

(6) Yana shigar da dare cikin rana, Yana kuma shigar da rana cikin dare. Kuma Shi Masanin abubuwan da suke cikin ƙiraza ne

(7) Ku yi imani da Allah da kuma Manzonsa, ku kuma ciyar daga abin da ya sanya ku wakilai a kansa, to waɗanda suka yi imani daga cikinku, suka kuma ciyar suna da lada mai girma

(8) Kuma me ya same ku ne ba kwa yin imani da Allah, alhali kuwa Manzo yana kiran ku don ku yi imani da Ubangijinku, haƙiƙa kuma kun yi masa alƙawari, in dai kun kasance muminai

(9) Shi ne Wanda Yake saukar da ayoyi bayyanannu ga Bawansa don Ya fitar da ku daga duffai zuwa haske. Kuma lalle Allah Mai tausayi ne, Mai rahama a gare ku

(10) Kuma me ya same ku ne da ba za ku ciyar saboda Allah ba, alhali kuwa gadon sammai da ƙasa na Allah ne? Wanda ya ciyar daga cikinku tun kafin buɗe (Makka)[2] ya kuma yi yaƙi, ba zai zama daidai (da wanda bai yi) ba. Waɗannan su suka fi girman daraja a kan waɗanda suka ciyar daga bisani, suka kuma yi yaƙi. Amma kuma kowannensu Allah Ya yi masa alƙawarin Aljanna. Allah kuma Masanin abin da kuke aikatawa ne

(11) Wane ne wanda zai bai wa Allah rance kyakkyawan rance, sai Ya ninka masa shi, alhali yana kuma da lada mai girma?

(1) Watau da iliminsa. Babu wani abu da yake vuya a gare shi, yana kuma ganin duk abin da suke aikatawa.

(2) Wasu daga cikin malamai sun fassara Fat'hu a wannan ayar da cewa ana nufin Sulhul Hudaibiyya.

يَوْمَ تَرَى ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ يَسْعَىٰ نُورُهُم بَيْنَ أَيْدِيهِمْ
وَبِأَيْمَٰنِهِم بُشْرَىٰكُمُ ٱلْيَوْمَ جَنَّٰتٌ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ
فِيهَا ۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿١٢﴾ يَوْمَ يَقُولُ ٱلْمُنَٰفِقُونَ وَٱلْمُنَٰفِقَٰتُ
لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱنظُرُونَا نَقْتَبِسْ مِن نُّورِكُمْ قِيلَ ٱرْجِعُوا۟ وَرَآءَكُمْ
فَٱلْتَمِسُوا۟ نُورًا ۖ فَضُرِبَ بَيْنَهُم بِسُورٍ لَّهُۥ بَابٌۢ بَاطِنُهُۥ فِيهِ ٱلرَّحْمَةُ
وَظَٰهِرُهُۥ مِن قِبَلِهِ ٱلْعَذَابُ ﴿١٣﴾ يُنَادُونَهُمْ أَلَمْ نَكُن مَّعَكُمْ ۖ قَالُوا۟ بَلَىٰ
وَلَٰكِنَّكُمْ فَتَنتُمْ أَنفُسَكُمْ وَتَرَبَّصْتُمْ وَٱرْتَبْتُمْ وَغَرَّتْكُمُ ٱلْأَمَانِىُّ
حَتَّىٰ جَآءَ أَمْرُ ٱللَّهِ وَغَرَّكُم بِٱللَّهِ ٱلْغَرُورُ ﴿١٤﴾ فَٱلْيَوْمَ لَا يُؤْخَذُ مِنكُمْ
فِدْيَةٌ وَلَا مِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ۚ مَأْوَىٰكُمُ ٱلنَّارُ ۖ هِىَ مَوْلَىٰكُمْ ۖ
وَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ﴿١٥﴾ ۞ أَلَمْ يَأْنِ لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَن تَخْشَعَ
قُلُوبُهُمْ لِذِكْرِ ٱللَّهِ وَمَا نَزَلَ مِنَ ٱلْحَقِّ وَلَا يَكُونُوا۟ كَٱلَّذِينَ
أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ مِن قَبْلُ فَطَالَ عَلَيْهِمُ ٱلْأَمَدُ فَقَسَتْ قُلُوبُهُمْ ۖ وَكَثِيرٌ
مِّنْهُمْ فَٰسِقُونَ ﴿١٦﴾ ٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ يُحْىِ ٱلْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا ۚ قَدْ بَيَّنَّا
لَكُمُ ٱلْءَايَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿١٧﴾ إِنَّ ٱلْمُصَّدِّقِينَ وَٱلْمُصَّدِّقَٰتِ
وَأَقْرَضُوا۟ ٱللَّهَ قَرْضًا حَسَنًا يُضَٰعَفُ لَهُمْ وَلَهُمْ أَجْرٌ كَرِيمٌ ﴿١٨﴾

(12) (Ka tuna) ranar da za ka ga muminai maza da muminai mata haskensu yana tafiya ta gabansu da ta damansu, (ana cewa da su): “Albishirinku a wannan rana (su ne) gidajen Aljanna da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, kuna masu dawwama a cikinsu. Wannan shi ne rabo mai girma.”

(13) A ranar da munafukai maza da munafukai mata za su riƙa cewa da waɗanda suka yi imani: “Ku saurara mana mu ɗan ɗosani haskenku.” Aka ce (da su): “Ku koma bayanku (watau duniya) sai ku nemi haske.” sai aka raba tsakaninsu da katanga wadda take da wata ƙofa, daga cikinta akwai rahama, bayanta kuma azaba ce (take bugowa) daga gare ta

(14) (Munafukan) suna kiran su cewa: “Yanzu ba mu kasance a tare da ku ba ne?” Suka ce: “Haka ne, sai dai ku kuma kun fitini kanku (da munafunci) kuka kuma saurari (aukuwar mummunan abu ga muminai), kuka kuma yi shakka (game da addini), burace-burace kuma suka ruɗe ku har mutuwa ta zo, Shaiɗan kuma ya ruɗe ku game da Allah

(15) “To a yau ba za a karɓi wata fansa ba daga gare ku da kuma daga waɗanda suka kafirta. Makomarku wuta; ita ce ta kamace ku, makoma kuwa ta munana.”

(16) Yanzu lokaci bai yi ba ga waɗanda suka yi imani zukatansu su yi taushi da zikirin Allah da kuma abin da Ya saukar na gaskiya, kuma kada su zama kamar waɗanda aka bai wa Littafi tun gabaninsu, sai lokaci ya tsawaita a gare su, sai zukatansu suka ƙeƙashe; mafiya yawa kuma daga cikinsu fasiƙai ne?

(17) Ku sani cewa Allah Yana raya ƙasa bayan mutuwarta[1]. Haƙiƙa Mun bayyana muku ayoyi don ku hankalta

(18) Lalle masu yin sadaka maza da masu yin sadaka mata, suka kuma bai wa Allah kyakkyawan rance, to za a ninninka musu shi, suna kuma da wani ladan mai daraja

(1) Watau hakanan Alqur’ani yake raya zukata bayan sun qeqashe.

وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦٓ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصِّدِّيقُونَ ۖ وَٱلشُّهَدَآءُ
عِندَ رَبِّهِمْ لَهُمْ أَجْرُهُمْ وَنُورُهُمْ ۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَكَذَّبُوا۟
بِـَٔايَٰتِنَآ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَحِيمِ ﴿١٩﴾ ٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّمَا ٱلْحَيَوٰةُ
ٱلدُّنْيَا لَعِبٌ وَلَهْوٌ وَزِينَةٌ وَتَفَاخُرٌۢ بَيْنَكُمْ وَتَكَاثُرٌ فِى ٱلْأَمْوَٰلِ
وَٱلْأَوْلَٰدِ ۖ كَمَثَلِ غَيْثٍ أَعْجَبَ ٱلْكُفَّارَ نَبَاتُهُۥ ثُمَّ يَهِيجُ فَتَرَىٰهُ
مُصْفَرًّا ثُمَّ يَكُونُ حُطَٰمًا ۖ وَفِى ٱلْءَاخِرَةِ عَذَابٌ شَدِيدٌ وَمَغْفِرَةٌ
مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضْوَٰنٌ ۚ وَمَا ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَآ إِلَّا مَتَٰعُ ٱلْغُرُورِ ﴿٢٠﴾
سَابِقُوٓا۟ إِلَىٰ مَغْفِرَةٍ مِّن رَّبِّكُمْ وَجَنَّةٍ عَرْضُهَا كَعَرْضِ ٱلسَّمَآءِ
وَٱلْأَرْضِ أُعِدَّتْ لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ ۚ ذَٰلِكَ فَضْلُ
ٱللَّهِ يُؤْتِيهِ مَن يَشَآءُ ۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلْفَضْلِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٢١﴾ مَآ أَصَابَ
مِن مُّصِيبَةٍ فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا فِىٓ أَنفُسِكُمْ إِلَّا فِى كِتَٰبٍ مِّن
قَبْلِ أَن نَّبْرَأَهَآ ۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ ﴿٢٢﴾ لِّكَيْلَا
تَأْسَوْا۟ عَلَىٰ مَا فَاتَكُمْ وَلَا تَفْرَحُوا۟ بِمَآ ءَاتَىٰكُمْ ۗ وَٱللَّهُ
لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخْتَالٍ فَخُورٍ ﴿٢٣﴾ ٱلَّذِينَ يَبْخَلُونَ وَيَأْمُرُونَ
ٱلنَّاسَ بِٱلْبُخْلِ ۗ وَمَن يَتَوَلَّ فَإِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْغَنِىُّ ٱلْحَمِيدُ ﴿٢٤﴾

(19) Waɗanda kuma suka yi imani da Allah da manzanninsa, waɗannan su ne siddiƙai; shahidai kuma suna da ladansu da haskensu a wurin Ubangijinsu; waɗanda kuwa suka kafirta suke kuma ƙaryata ayoyinmu, to waɗannan su ne ‘yan (wutar) Jahimu

(20) Ku sani cewa, ita dai rayuwar duniya ba wata aba ba ce sai wasa da sharholiya da ƙyale-ƙyale da kuma fariya a tsakaninku da takara wajan nuna yawan dukiya da ‘ya’yaye; ta yi kama da ruwan saman da tsirransa suka bai wa manoma sha’awa, sannan duk ya bushe, sai ka gan shi fatsi-fatsi, sannan kuma ya zama dudduga; a lahira kuwa akwai azaba mai tsanani da gafara daga Allah da kuma yarda. Rayuwar duniya ba komai ba ce sai jin daɗi mai ruɗi

(21) Ku yi rige-rige zuwa neman gafara daga Ubangijinku da Aljanna wadda faɗinta kamar faɗin sammai da ƙasa yake, an tanade ta don waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa. Wannan falalar Allah ce da Yake ba da ita ga wanda Ya ga dama. Allah kuwa Ma’abocin falala ne, Mai girma

(22) Babu wani abu da ya samu na musiba a bayan ƙasa, ko kuma ga kawunanku face yana cikin Littafin (Lauhul Mahafuzu) tun kafin Mu halicce ta (watau halittar). Lalle wannan (a wurin Allah) mai sauƙi ne

(23) Don kada ku yi baƙin ciki a kan abin da ya kuɓuce muku, kada kuma ku yi fariya da abin da Ya ba ku, Allah kuwa ba Ya son duk wani mai taƙama, mai fariya

(24) (Su ne) waɗanda suke yin rowa, suke kuma umartar mutane da yin rowar. Wanda kuwa ya ba da baya, to lalle Allah Shi Mawadaci ne, Sha-Yabo

لَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلَنَا بِالْبَيِّنَاتِ وَأَنزَلْنَا مَعَهُمُ الْكِتَابَ
وَالْمِيزَانَ لِيَقُومَ النَّاسُ بِالْقِسْطِ ۖ وَأَنزَلْنَا الْحَدِيدَ فِيهِ
بَأْسٌ شَدِيدٌ وَمَنَافِعُ لِلنَّاسِ وَلِيَعْلَمَ اللَّهُ مَن يَنصُرُهُ وَرُسُلَهُ
بِالْغَيْبِ ۚ إِنَّ اللَّهَ قَوِيٌّ عَزِيزٌ ﴿٢٥﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا نُوحًا وَإِبْرَاهِيمَ
وَجَعَلْنَا فِي ذُرِّيَّتِهِمَا النُّبُوَّةَ وَالْكِتَابَ ۖ فَمِنْهُم مُّهْتَدٍ ۖ
وَكَثِيرٌ مِّنْهُمْ فَاسِقُونَ ﴿٢٦﴾ ثُمَّ قَفَّيْنَا عَلَىٰ آثَارِهِم
بِرُسُلِنَا وَقَفَّيْنَا بِعِيسَى ابْنِ مَرْيَمَ وَآتَيْنَاهُ الْإِنجِيلَ ۖ وَجَعَلْنَا
فِي قُلُوبِ الَّذِينَ اتَّبَعُوهُ رَأْفَةً وَرَحْمَةً ۚ وَرَهْبَانِيَّةً
ابْتَدَعُوهَا مَا كَتَبْنَاهَا عَلَيْهِمْ إِلَّا ابْتِغَاءَ رِضْوَانِ اللَّهِ
فَمَا رَعَوْهَا حَقَّ رِعَايَتِهَا ۖ فَآتَيْنَا الَّذِينَ آمَنُوا مِنْهُمْ أَجْرَهُمْ ۖ
وَكَثِيرٌ مِّنْهُمْ فَاسِقُونَ ﴿٢٧﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا اتَّقُوا اللَّهَ
وَآمِنُوا بِرَسُولِهِ يُؤْتِكُمْ كِفْلَيْنِ مِن رَّحْمَتِهِ وَيَجْعَل لَّكُمْ نُورًا
تَمْشُونَ بِهِ وَيَغْفِرْ لَكُمْ ۚ وَاللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٢٨﴾ لِّئَلَّا يَعْلَمَ
أَهْلُ الْكِتَابِ أَلَّا يَقْدِرُونَ عَلَىٰ شَيْءٍ مِّن فَضْلِ اللَّهِ وَأَنَّ
الْفَضْلَ بِيَدِ اللَّهِ يُؤْتِيهِ مَن يَشَاءُ ۚ وَاللَّهُ ذُو الْفَضْلِ الْعَظِيمِ ﴿٢٩﴾

(25) Hakika Mun aiko manzanninmu da (ayoyi) mabayyana, Muka kuma saukar da littafi da ma'auni a tare da su (manzannin) don mutane su tsaya da adalci; Muka kuma saukar da bakin karfe wanda a tare da shi akwai tsananin karfi da kuma amfani ga mutane, don kuma Allah Ya bayyanar da wanda yake taimakon Sa da manzanninsa a boye. Lalle Allah Mai karfi ne, Mabuwayi

(26) Hakika kuma Mun aiko Nuhu da Ibrahimu, Muka kuma sanya annabta da littafi cikin zuriyarsu; To daga cikinsu akwai shiryayyu, masu yawa kuwa daga cikinsu fasikai ne

(27) Sannan a bayansu Muka biyar da manzanninmu, Muka kuma biyar da Isa dan Maryamu Muka kuma ba shi Linjila, kuma Muka sanya jin kai da rahama a cikin zukatan wadanda suka bi shi. Rahbaniyanci(1) kuma su ne suka kago shi, ba Mu wajabta musu shi ba, sai dai (Mun wajabta musu) neman yardar Allah, amma ba su kiyaye shi ba kamar yadda ya kamata; sai Muka bai wa wadanda suka yi imani daga cikinsu ladansu; da yawa kuwa fasikai ne


(28) Ya ku wadanda suka imani, ku kiyaye dokokin Allah, ku kuma yi imani da Manzonsa, zai ba ku ribi biyu na rahamarsa, Ya kuma sanya muku haske da za ku rika tafiya da shi, kuma Ya gafarta muku. Domin kuwa Allah Mai gafara ne, Mai rahama

(29) Don ma'abota littafi su san cewa ba su da hannu a falalar Allah, don ko lalle falala a hannun Allah take, Yana ba da ita ga wanda Ya ga dama. Allah kuma Ma'abocin babbar falala ne

(1) Bidi'ar Rahbaniyanci ita ce, qaurace wa aure da barin cin daxaxan abubuwa na halal da haramta wa kai wasu abubuwa da Allah ya halatta.



Sura Mujadila



(1) Hakika Allah ya ji zancen wadda take muhawara da kai game da (lamarin) mijinta[1], tana kuma kai kara zuwa ga Allah, Allah kuma Yana jin muhawararku. Lalle Allah Mai ji ne, Mai gani

(2) Wadanda suke yin zihari[2] daga cikinku ga matansu, su ba iyayensu mata ba ne; iyayensu mata su ne wadanda kawai suka haife su. Lalle kuma su tabbas suna fadar muguwar magana ne da tsagwaron karya. Kuma lalle Allah tabbas Mai afuwa ne, Mai gafara

(3) Wadanda kuwa suke yin zihari ga matansu sannan suka yi niyyar janye abin da suka fada, to sai su 'yanta wuyaye (bawa namiji ko mace), tun kafin su sadu. Wannan (shi ne abin da) ake yi muku wa'azi da shi. Allah kuma Masanin abin da kuke aikatawa ne

(4) Sannan wanda bai samu ba, to sai ya yi azumin wata biyu a jere tun kafin su sadu; sannan wanda bai sami iko ba sai ya ciyar da miskini sittin. Wannan kuwa don ku yi imani da Allah da Manzonsa. Wadannan kuma su ne iyakokin Allah. Kafirai kuma suna da azaba mai radadi

(5) Lalle wadanda suke saba wa Allah da Manzonsa an kaskantar da su kamar yadda aka kaskantar da wadanda suke gabaninsu. Kuma hakika Mun saukar da ayoyi bayyanannu. Kafirai kuma suna da azaba mai wulakantarwa

(6) A ranar da Allah zai tashe su gaba daya, sannan Ya ba su labarin abin da suka aikata. Allah Ya kididdige shi, su kuwa sun manta shi. Allah kuwa Mai ganin kowane abu ne

(1) Ita ce Khaulatu 'yar Sa'alaba ( ), mijinta kuwa shi ne Ausu dan Samit ( ).

(2) Shi ne miji ya kwatanta matarsa da mahaifiyarsa ya ce: "Ke a wurina kamar bayan mahaifiyata ne". A zamanin jahiliyya idan miji ya fada wa matarsa haka, to ta haramta a gare shi har abada.

أَلَمْ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۖ مَا يَكُونُ مِن
نَّجْوَىٰ ثَلَٰثَةٍ إِلَّا هُوَ رَابِعُهُمْ وَلَا خَمْسَةٍ إِلَّا هُوَ سَادِسُهُمْ وَلَآ أَدْنَىٰ
مِن ذَٰلِكَ وَلَآ أَكْثَرَ إِلَّا هُوَ مَعَهُمْ أَيْنَ مَا كَانُوا۟ ۖ ثُمَّ يُنَبِّئُهُم بِمَا
عَمِلُوا۟ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿٧﴾ أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ
نُهُوا۟ عَنِ ٱلنَّجْوَىٰ ثُمَّ يَعُودُونَ لِمَا نُهُوا۟ عَنْهُ وَيَتَنَٰجَوْنَ بِٱلْإِثْمِ
وَٱلْعُدْوَٰنِ وَمَعْصِيَتِ ٱلرَّسُولِ ۖ وَإِذَا جَآءُوكَ حَيَّوْكَ بِمَا لَمْ يُحَيِّكَ
بِهِ ٱللَّهُ وَيَقُولُونَ فِىٓ أَنفُسِهِمْ لَوْلَا يُعَذِّبُنَا ٱللَّهُ بِمَا نَقُولُ ۚ حَسْبُهُمْ
جَهَنَّمُ يَصْلَوْنَهَا ۖ فَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ﴿٨﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِذَا
تَنَٰجَيْتُمْ فَلَا تَتَنَٰجَوْا۟ بِٱلْإِثْمِ وَٱلْعُدْوَٰنِ وَمَعْصِيَتِ ٱلرَّسُولِ
وَتَنَٰجَوْا۟ بِٱلْبِرِّ وَٱلتَّقْوَىٰ ۖ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ٱلَّذِىٓ إِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ﴿٩﴾ إِنَّمَا
ٱلنَّجْوَىٰ مِنَ ٱلشَّيْطَٰنِ لِيَحْزُنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَلَيْسَ بِضَآرِّهِمْ
شَيْـًٔا إِلَّا بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ ٱلْمُؤْمِنُونَ ﴿١٠﴾ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِذَا قِيلَ لَكُمْ تَفَسَّحُوا۟ فِى ٱلْمَجَٰلِسِ فَٱفْسَحُوا۟ يَفْسَحِ
ٱللَّهُ لَكُمْ ۖ وَإِذَا قِيلَ ٱنشُزُوا۟ فَٱنشُزُوا۟ يَرْفَعِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مِنكُمْ
وَٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْعِلْمَ دَرَجَٰتٍ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ﴿١١﴾

(7) Shin ba ka sani ba ne cewa Allah Ya san abin da yake cikin sammai da abi da yake cikin ƙasa? Babu wata ganawa tsakanin mutum uku da za ta faru sai Shi ne na huɗunsu[1], da kuma (tsakanin mutum) biyar sai Shi ne na shidansu, da kuma abin da ya kasa (haka) ko ya fi, sai Shi (Allah) Yana tare da su a duk inda suke[2]; sannan Ya ba su labarin abin da suka aikata a ranar alƙiyama. Lalle Allah Masanin komai ne

(8) Shin ba ka ga waɗanda aka hana su ganawa ba, sannan suke koma wa abin da aka hane su yinsa, suke kuma ganawa a kan saɓo da ta'addanci, da kuma saba wa Manzo? Idan kuma suka zo wurinka sai su gaishe ka da lafazin da Allah bai gaishe ka da shi ba[3], su riƙa cewa a ransu: "Me ya hana Allah Ya azabtar da mu saboda abin da muka faɗa?" Jahannama ta ishe su, za su shige ta; saboda haka makoma ta munana

(9) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan za ku gana to kada ku yi ganawar saɓo da ta'addanci da kuma saba wa Manzo. (A maimakon haka) ku gana a kan ayyukan alheri da taƙawa; kuma ku kiyaye dokokin Allah wanda zuwa gare Shi ne za a tattaro ku

(10) Ganawar (tasu) kawai daga Shaiɗan take, don ya baƙanta ran waɗanda suka yi imani, ba kuwa zai cuce su da komai ba sai da izinin Allah. Ga Allah ne kuma muminai za su dogara

(11) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan aka ce da ku: "Ku yalwata a wuraren zama," to sai ku yalwata, Allah zai yalwata muku[4]; idan kuma aka ce: "Ku tashi (daga wurinku)[5]," to sai ku tashi, Allah zai ɗaga darajojin waɗanda suka yi imani daga cikinku da waɗanda aka bai wa ilimi. Allah kuma Masanin abin da kuke aikatawa ne

(1) Watau da iliminsa.

(2) Watau yana tare da su da saninsa da ganinsa.

(3) Watau suna ce masa: Assamu alaika, ma'ana mutuwa ta tabbata a kanka.

(4) Watau zai buɗa musu a rayuwarsu ta duniya da ta lahira.

(5) Watau domin wani aiki na addini ko wata buƙata da ta taso.

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا نَٰجَيۡتُمُ ٱلرَّسُولَ فَقَدِّمُواْ بَيۡنَ يَدَيۡ نَجۡوَىٰكُمۡ
صَدَقَةٗۚ ذَٰلِكَ خَيۡرٞ لَّكُمۡ وَأَطۡهَرُۚ فَإِن لَّمۡ تَجِدُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٌ
١٢ ءَأَشۡفَقۡتُمۡ أَن تُقَدِّمُواْ بَيۡنَ يَدَيۡ نَجۡوَىٰكُمۡ صَدَقَٰتٖۚ فَإِذۡ لَمۡ تَفۡعَلُواْ
وَتَابَ ٱللَّهُ عَلَيۡكُمۡ فَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ
وَرَسُولَهُۥۚ وَٱللَّهُ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ١٣ ۞أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ تَوَلَّوۡاْ
قَوۡمًا غَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِم مَّا هُم مِّنكُمۡ وَلَا مِنۡهُمۡ وَيَحۡلِفُونَ عَلَى ٱلۡكَذِبِ
وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ١٤ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُمۡ عَذَابٗا شَدِيدًاۖ إِنَّهُمۡ سَآءَ مَا كَانُواْ
يَعۡمَلُونَ ١٥ ٱتَّخَذُوٓاْ أَيۡمَٰنَهُمۡ جُنَّةٗ فَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ فَلَهُمۡ
عَذَابٞ مُّهِينٞ ١٦ لَّن تُغۡنِيَ عَنۡهُمۡ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُم مِّنَ ٱللَّهِ
شَيۡـٔٗاۚ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ١٧ يَوۡمَ يَبۡعَثُهُمُ
ٱللَّهُ جَمِيعٗا فَيَحۡلِفُونَ لَهُۥ كَمَا يَحۡلِفُونَ لَكُمۡ وَيَحۡسَبُونَ أَنَّهُمۡ
عَلَىٰ شَيۡءٍۚ أَلَآ إِنَّهُمۡ هُمُ ٱلۡكَٰذِبُونَ ١٨ ٱسۡتَحۡوَذَ عَلَيۡهِمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ
فَأَنسَىٰهُمۡ ذِكۡرَ ٱللَّهِۚ أُوْلَٰٓئِكَ حِزۡبُ ٱلشَّيۡطَٰنِۚ أَلَآ إِنَّ حِزۡبَ ٱلشَّيۡطَٰنِ
هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ١٩ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُحَآدُّونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ أُوْلَٰٓئِكَ فِي ٱلۡأَذَلِّينَ
٢٠ كَتَبَ ٱللَّهُ لَأَغۡلِبَنَّ أَنَا۠ وَرُسُلِيٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ قَوِيٌّ عَزِيزٞ ٢١

(12) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan za ku gana da Manzo, to sai ku gabatar da wata sadaka kafin ganawar taku. Wannan shi ya fi muku alheri da tsarkaka. Sannan idan ba ku samu ba, to lalle Allah Mai gafara ne, Mai rahama

(13) Yanzu kun samu damuwa ne ta gabatar da sadaka kafin ganawarku? To idan ba ku aikata haka ba Allah kuma ya karɓi tubarku, to sai ku tsayar da salla, ku ba da zakka, ku kuma bi Allah da Manzonsa. Allah kuma Masanin abin da kuke aikatawa ne

(14) Shin ba ka ga waɗanda suka yi abota da wasu mutane da Allah Ya yi fushi da su[1] ba, su ba cikinku suke ba, ba kuma cikinsu suke ba; su kuma rika rantsuwa a kan ƙarya, alhali kuwa su suna sane (da yin ta)?

(15) Allah Ya tanadar musu azaba mai tsanani, lalle su abin da suke aikatawa ya munana

(16) Sun ɗauki rantse-rantsensu su zama garkuwa, sai suka kange hanyar Allah, saboda haka suna da (sakamakon) azaba mai wulaƙantarwa

(17) Dukiyoyinsu da 'ya'yansu ba za su amfanar musu komai ba a wurin Allah. Waɗannan su ne 'yan wuta; su madawwama ne a cikinta

(18) A ranar da Allah zai tashe su baki ɗaya sai su rantse Masa kamar yadda suke rantse muku, su kuma rika tsammanin su sun yi wani abu (mai amfani). Ku saurara, lalle kam su ne maƙaryata

(19) Shaiɗan ya ci ƙarfinsu, sai ya mantar da su ambaton Allah. Waɗannan su ne ƙungiyar Shaiɗan. Ku saurara, lalle ƙungiyar Shaiɗan su ne taɓaɓɓu

(20) Lalle waɗanda suke saɓa wa Allah da Manzonsa waɗannan suna cikin mafiya ƙasƙanci

(21) Allah Ya rubuta cewa: Lalle Ni da manzannina ne za mu yi galaba. Lalle Allah Mai ƙarfi ne, Mabuwayi

(1) Su ne Yahudawa waɗanda munafukai suke abota da su.

لَّا تَجِدُ قَوْمًا يُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ وَالْيَوْمِ الْآخِرِ يُوَادُّونَ مَنْ حَادَّ
اللَّهَ وَرَسُولَهُ وَلَوْ كَانُوا آبَاءَهُمْ أَوْ أَبْنَاءَهُمْ أَوْ إِخْوَانَهُمْ
أَوْ عَشِيرَتَهُمْ أُولَٰئِكَ كَتَبَ فِي قُلُوبِهِمُ الْإِيمَانَ وَأَيَّدَهُم
بِرُوحٍ مِّنْهُ وَيُدْخِلُهُمْ جَنَّاتٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ
خَالِدِينَ فِيهَا رَضِيَ اللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا عَنْهُ أُولَٰئِكَ حِزْبُ
اللَّهِ أَلَا إِنَّ حِزْبَ اللَّهِ هُمُ الْمُفْلِحُونَ ﴿٢٢﴾

سُورَةُ الْحَشْرِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ وَهُوَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ
﴿١﴾ هُوَ الَّذِي أَخْرَجَ الَّذِينَ كَفَرُوا مِنْ أَهْلِ الْكِتَابِ مِن دِيَارِهِمْ
لِأَوَّلِ الْحَشْرِ مَا ظَنَنتُمْ أَن يَخْرُجُوا وَظَنُّوا أَنَّهُم مَّانِعَتُهُمْ
حُصُونُهُم مِّنَ اللَّهِ فَأَتَاهُمُ اللَّهُ مِنْ حَيْثُ لَمْ يَحْتَسِبُوا وَقَذَفَ
فِي قُلُوبِهِمُ الرُّعْبَ يُخْرِبُونَ بُيُوتَهُم بِأَيْدِيهِمْ وَأَيْدِي الْمُؤْمِنِينَ
فَاعْتَبِرُوا يَا أُولِي الْأَبْصَارِ ﴿٢﴾ وَلَوْلَا أَن كَتَبَ اللَّهُ عَلَيْهِمُ
الْجَلَاءَ لَعَذَّبَهُمْ فِي الدُّنْيَا وَلَهُمْ فِي الْآخِرَةِ عَذَابُ النَّارِ ﴿٣﴾

(22) Ba za ka taɓa samun wasu mutane da suke yin imani da Allah da ranar lahira ba, su riƙa ƙaunar waɗanda suke gaba da Allah da Manzonsa, ko da kuwa sun kasance iyayensu ne ko ‘ya’yansu ko ‘yan’uwansu ko kuma danginsu. Waɗannan Allah Ya rubuta imani a cikin zukatansu, Ya kuma ƙarfafe su da wani ruhi daga wurinsa[1]; zai kuma shigar da su gidajen Aljanna (waɗanda) ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, madawwama a cikinsu. Allah Ya yarda da su, su ma sun yarda da Shi. Waɗannan ne ƙungiyar Allah. Ku saurara, lalle ƙungiyar Allah su ne masu samun babban rabo

Sura Hashr

(1) Abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa ya tsarkake Allah; Shi ne kuwa Mabuwayi, Mai hikima
(2) Shi ne wanda Ya fitar da waɗanda suka kafirce daga ma’abota littafi[1] daga gidajensu a fitarwa ta farko. Ba ku yi tsammanin cewa za su fita ba, su kuma sun zaci ganuwoyinsu za su kare su daga Allah, sai Allah Ya zo musu ta inda ba su yi tsammani ba; Ya kuma jefa tsoro a cikin zukatansu. Suka riƙa rushe gidajensu da hannayensu da kuma hannayen muminai, to sai ku luru da kyau ya ku ma’abota basira
(3) Ba don Allah Ya ƙaddara musu ficewa ba, lalle da Ya azabtar da su a duniya, a lahira kuma suna da azabar wuta

(1) Watau zai ƙarfafe su da wata hujja daga wurinsa da haske.

(2) Su ne Yahudawan Banun Nadhir waɗanda Annabi ( ) ya kore su daga Madina bayan sun yi yunƙurin kashe shi.

ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ شَآقُّوا۟ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ ۖ وَمَن يُشَآقِّ ٱللَّهَ فَإِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ
ٱلْعِقَابِ ﴿٤﴾ مَا قَطَعْتُم مِّن لِّينَةٍ أَوْ تَرَكْتُمُوهَا قَآئِمَةً عَلَىٰٓ
أُصُولِهَا فَبِإِذْنِ ٱللَّهِ وَلِيُخْزِىَ ٱلْفَٰسِقِينَ ﴿٥﴾ وَمَآ أَفَآءَ ٱللَّهُ
عَلَىٰ رَسُولِهِۦ مِنْهُمْ فَمَآ أَوْجَفْتُمْ عَلَيْهِ مِنْ خَيْلٍ وَلَا رِكَابٍ
وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يُسَلِّطُ رُسُلَهُۥ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ ۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ
قَدِيرٌ ﴿٦﴾ مَّآ أَفَآءَ ٱللَّهُ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ مِنْ أَهْلِ ٱلْقُرَىٰ فَلِلَّهِ وَلِلرَّسُولِ
وَلِذِى ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينِ وَٱبْنِ ٱلسَّبِيلِ كَىْ لَا يَكُونَ
دُولَةًۢ بَيْنَ ٱلْأَغْنِيَآءِ مِنكُمْ ۚ وَمَآ ءَاتَىٰكُمُ ٱلرَّسُولُ فَخُذُوهُ
وَمَا نَهَىٰكُمْ عَنْهُ فَٱنتَهُوا۟ ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ
﴿٧﴾ لِلْفُقَرَآءِ ٱلْمُهَٰجِرِينَ ٱلَّذِينَ أُخْرِجُوا۟ مِن دِيَٰرِهِمْ وَأَمْوَٰلِهِمْ
يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضْوَٰنًا وَيَنصُرُونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ ۚ
أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصَّٰدِقُونَ ﴿٨﴾ وَٱلَّذِينَ تَبَوَّءُو ٱلدَّارَ وَٱلْإِيمَٰنَ مِن
قَبْلِهِمْ يُحِبُّونَ مَنْ هَاجَرَ إِلَيْهِمْ وَلَا يَجِدُونَ فِى صُدُورِهِمْ
حَاجَةً مِّمَّآ أُوتُوا۟ وَيُؤْثِرُونَ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ وَلَوْ كَانَ بِهِمْ خَصَاصَةٌ ۚ
وَمَن يُوقَ شُحَّ نَفْسِهِۦ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ﴿٩﴾

(4) Wannan kuwa saboda cewa sun saba wa Allah da Manzonsa ne, duk kuwa wanda ya saba wa Allah da Manzonsa, to lalle Allah Mai tsananin ukuba ne

(5) Duk abin da kuka sare na wata bishiyar dabino ko kuka bar ta a tsaye a kan tushiyoyinta, to da izinin Allah ne, don kuma Ya kunyata fasikai

(6) Kuma duk abin da Allah Ya bai wa Manzonsa na wata dukiya tasu (don falalarsa), to ba wani hari kuka kai na dawaki ko rakuma[1] ba saboda shi, sai dai kuma Allah Shi ne Yake ɗora manzanninsa a kan wanda Ya ga dama. Allah kuwa Mai iko ne a kan komai

(7) Abin da Allah ya bai wa Manzonsa na wata dukiya daga mutanen alkaryu, to na Allah ne da Manzonsa da kuma danginsa na kusa[2] da marayu da miskinai da matafiyin (da guzuri ya yanke wa), don kada ya zama mai juyawa tsakanin mawadata daga cikinku. Kuma abin da Manzo ya ba ku sai ku karɓe shi, abin kuma da ya hana ku sai ku hanu. Ku kuma kiyaye dokokin Allah; lalle Allah Mai tsananin ukuba ne

(8) (Za a bayar da dukiyar) ga matalauta da suka yi hijira waɗanda aka fitar da su daga gidajensu da dukiyoyinsu don neman falala daga Allah da yardarsa, suna kuma taimakon (addinin) Allah da Manzonsa. Waɗannan su ne masu gaskiya

(9) Da kuma waɗanda suka tanadi gida (mutanen Madina) suka kuma (karɓi) imani gabaninsu (masu hijira), suna son waɗanda suka yi hijira zuwa gare su, ba sa samun wani ƙyashi a zukatansu game da abin da aka ba su (masu hijira), suna kuma fifita (masu hijira) a kan kawunansu, ko da kuwa suna da tsananin buƙata. Duk kuwa wanda aka kiyaye shi daga son kansa, to waɗannan su ne masu babban rabo

(1) Watau ku sami dukiya ba tare da yaƙi ba.

(2) Watau Banu Hashim da Banul Muɗɗalib, waɗanda aka haramta musu karɓar sadaka ko zakka.

وَٱلَّذِينَ جَآءُو مِنۢ بَعۡدِهِمۡ يَقُولُونَ رَبَّنَا ٱغۡفِرۡ لَنَا وَلِإِخۡوَٰنِنَا
ٱلَّذِينَ سَبَقُونَا بِٱلۡإِيمَٰنِ وَلَا تَجۡعَلۡ فِي قُلُوبِنَا غِلّٗا لِّلَّذِينَ
ءَامَنُواْ رَبَّنَآ إِنَّكَ رَءُوفٞ رَّحِيمٌ ١٠ ۞ أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ
نَافَقُواْ يَقُولُونَ لِإِخۡوَٰنِهِمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ
لَئِنۡ أُخۡرِجۡتُمۡ لَنَخۡرُجَنَّ مَعَكُمۡ وَلَا نُطِيعُ فِيكُمۡ أَحَدًا أَبَدٗا
وَإِن قُوتِلۡتُمۡ لَنَنصُرَنَّكُمۡ وَٱللَّهُ يَشۡهَدُ إِنَّهُمۡ لَكَٰذِبُونَ
١١ لَئِنۡ أُخۡرِجُواْ لَا يَخۡرُجُونَ مَعَهُمۡ وَلَئِن قُوتِلُواْ لَا يَنصُرُونَهُمۡ
وَلَئِن نَّصَرُوهُمۡ لَيُوَلُّنَّ ٱلۡأَدۡبَٰرَ ثُمَّ لَا يُنصَرُونَ ١٢ لَأَنتُمۡ
أَشَدُّ رَهۡبَةٗ فِي صُدُورِهِم مِّنَ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ
لَّا يَفۡقَهُونَ ١٣ لَا يُقَٰتِلُونَكُمۡ جَمِيعًا إِلَّا فِي قُرٗى مُّحَصَّنَةٍ
أَوۡ مِن وَرَآءِ جُدُرِۭۚ بَأۡسُهُم بَيۡنَهُمۡ شَدِيدٞۚ تَحۡسَبُهُمۡ جَمِيعٗا
وَقُلُوبُهُمۡ شَتَّىٰۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ لَّا يَعۡقِلُونَ ١٤ كَمَثَلِ
ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ قَرِيبٗاۖ ذَاقُواْ وَبَالَ أَمۡرِهِمۡ وَلَهُمۡ عَذَابٌ
أَلِيمٞ ١٥ كَمَثَلِ ٱلشَّيۡطَٰنِ إِذۡ قَالَ لِلۡإِنسَٰنِ ٱكۡفُرۡ فَلَمَّا
كَفَرَ قَالَ إِنِّي بَرِيٓءٞ مِّنكَ إِنِّيٓ أَخَافُ ٱللَّهَ رَبَّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٦

(10) Duk kuma waɗanda suka zo daga bayansu suna cewa: “Ya Ubangijinmu, Ka gafarta mana mu da ‘yan’uwanmu waɗanda suka rigaye mu yin imani, kada kuma Ka sanya wata ƙullata a zukatanmu game da waɗanda suka yi imani, ya Ubangijinmu, lalle Kai Mai tausayawa ne, Mai jin ƙai.”

(11) Ba ka ga waɗanda suka yi munafunci suna ce wa ‘yan’uwansu waɗanda suka kafirta daga ma’abota littafi: “Tabbas idan aka fitar da ku, lalle za mu fita tare da ku, ba kuma za mu bi wani mutum game da ku ba har adaba, kuma idan aka yaƙe ku tabbas za mu taimake ku.” Allah kuma Ya san tabbas ƙarya suke yi

(12) Tabbas idan aka fitar da su ba za su fita tare da su ba, kuma tabbas idan aka yaƙe su ba za su taimake su ba, tabbas kuwa idan ma sun taimake su ɗin, lalle za su gudu su ba da baya, sannan kuma ba za a ba su nasara ba

(13) Tabbas ku suka fi tsoro a zukatansu fiye da Allah. Wannan kuwa saboda su mutane ne da ba sa fahimta

(14) Ba sa yaƙar ku a tare sai a cikin wasu alƙaryu katangaggu ko ta bayan katangu. Yaƙi a tsakaninsu mai tsanani ne. Za ka tsammaci kansu a haɗe yake, alhali zukatansu a rarrabe suke. Wannan kuwa saboda cewar su mutane ne da ba sa hankalta

(15) Sun yi kama da waɗanda suke a gabaninsu ba da daɗewa ba, sun ɗanɗani azabar al’amarinsu, suna kuma da (sakamakon) azaba mai raɗaɗi

(16) Sun yi kama da Shaiɗan lokacin da ya ce wa mutum: “Ka kafirta.” To yayin da ya kafirta sai ya ce: “Lalle ni ba ruwana da kai, lalle ni ina tsoron Allah Ubangijin talikai.”

فَكَانَ عَٰقِبَتَهُمَآ أَنَّهُمَا فِى ٱلنَّارِ خَٰلِدَيْنِ فِيهَا ۚ وَذَٰلِكَ جَزَٰٓؤُا۟
ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٧﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَلْتَنظُرْ نَفْسٌ
مَّا قَدَّمَتْ لِغَدٍ ۖ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرٌۢ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿١٨﴾
وَلَا تَكُونُوا۟ كَٱلَّذِينَ نَسُوا۟ ٱللَّهَ فَأَنسَىٰهُمْ أَنفُسَهُمْ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ
هُمُ ٱلْفَٰسِقُونَ ﴿١٩﴾ لَا يَسْتَوِىٓ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ وَأَصْحَٰبُ
ٱلْجَنَّةِ ۚ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ هُمُ ٱلْفَآئِزُونَ ﴿٢٠﴾ لَوْ أَنزَلْنَا هَٰذَا
ٱلْقُرْءَانَ عَلَىٰ جَبَلٍ لَّرَأَيْتَهُۥ خَٰشِعًا مُّتَصَدِّعًا مِّنْ خَشْيَةِ
ٱللَّهِ ۚ وَتِلْكَ ٱلْأَمْثَٰلُ نَضْرِبُهَا لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَتَفَكَّرُونَ
﴿٢١﴾ هُوَ ٱللَّهُ ٱلَّذِى لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ عَٰلِمُ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ ۖ
هُوَ ٱلرَّحْمَٰنُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٢٢﴾ هُوَ ٱللَّهُ ٱلَّذِى لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْمَلِكُ
ٱلْقُدُّوسُ ٱلسَّلَٰمُ ٱلْمُؤْمِنُ ٱلْمُهَيْمِنُ ٱلْعَزِيزُ ٱلْجَبَّارُ
ٱلْمُتَكَبِّرُ ۚ سُبْحَٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٢٣﴾ هُوَ ٱللَّهُ
ٱلْخَٰلِقُ ٱلْبَارِئُ ٱلْمُصَوِّرُ ۖ لَهُ ٱلْأَسْمَآءُ ٱلْحُسْنَىٰ ۚ يُسَبِّحُ
لَهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٢٤﴾

سُورَةُ الْمُمْتَحَنَةِ

(17) Sai ƙarshen al'amarinsu ya kasance cewa su duka biyun masu dawwama ne cikin wuta. Wannan kuwa shi ne sakamakon azzalumai

(18) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Allah, kuma kowane rai ya dubi abin da ya gabatar don gobe (lahira); ku kuma kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Masanin abin da kuke aikatawa ne

(19) Kada kuma ku zama kamar waɗanda suka manta da Allah, sai Ya mantar da su kawunansu. Waɗannan su ne fasiƙai

(20) 'Yan wuta da 'yan Aljanna ba za su yi daidai ba. 'Yan Aljanna su ne masu rabauta

(21) Da za Mu saukar da wannan Alƙur'ani ga wani dutse, da lalle ka gan shi yana mai ƙasƙantar da kai mai tsattsagewa don tsoron Allah. Waɗannan misalan Muna buga wa mutane su ne don su yi tunani

(22) Shi ne Allah wanda babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi; Masanin ɓoye da sarari; kuma Shi ne Mai rahama, Mai jin ƙai

(23) Shi ne Allah wanda babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi; Shi ne Sarki, Mai tsarki, Amintacce, Mai amintarwa, Mai kula da komai, Mabuwayi, Mai tsananin ƙarfi; Mai nuna isa. Allah Ya tsarkaka daga abin da suke tara (Shi da shi)

(24) Shi ne Allah Mahalicci, Mai ƙagawa Mai surantawa(1); Yana da sunaye mafiya kyau. Duk abin da yake cikin sammai da ƙasa yana tsarkake Shi; kuma Shi Mabuwayi ne, Mai hikima

(1) Watau mai suranta kamannin abin da ya halitta yadda ya ga dama.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ عَدُوِّي وَعَدُوَّكُمْ أَوْلِيَآءَ تُلْقُونَ
إِلَيْهِم بِٱلْمَوَدَّةِ وَقَدْ كَفَرُواْ بِمَا جَآءَكُم مِّنَ ٱلْحَقِّ يُخْرِجُونَ ٱلرَّسُولَ
وَإِيَّاكُمْ أَن تُؤْمِنُواْ بِٱللَّهِ رَبِّكُمْ إِن كُنتُمْ خَرَجْتُمْ جِهَٰدًا فِي سَبِيلِي
وَٱبْتِغَآءَ مَرْضَاتِي تُسِرُّونَ إِلَيْهِم بِٱلْمَوَدَّةِ وَأَنَا۠ أَعْلَمُ بِمَآ أَخْفَيْتُمْ
وَمَآ أَعْلَنتُمْ ۚ وَمَن يَفْعَلْهُ مِنكُمْ فَقَدْ ضَلَّ سَوَآءَ ٱلسَّبِيلِ ﴿١﴾ إِن
يَثْقَفُوكُمْ يَكُونُواْ لَكُمْ أَعْدَآءً وَيَبْسُطُوٓاْ إِلَيْكُمْ أَيْدِيَهُمْ وَأَلْسِنَتَهُم
بِٱلسُّوٓءِ وَوَدُّواْ لَوْ تَكْفُرُونَ ﴿٢﴾ لَن تَنفَعَكُمْ أَرْحَامُكُمْ وَلَآ أَوْلَٰدُكُمْ ۚ
يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يَفْصِلُ بَيْنَكُمْ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿٣﴾ قَدْ كَانَتْ
لَكُمْ أُسْوَةٌ حَسَنَةٌ فِيٓ إِبْرَٰهِيمَ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ ۚ إِذْ قَالُواْ لِقَوْمِهِمْ إِنَّا
بُرَءَٰٓؤُاْ مِنكُمْ وَمِمَّا تَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ كَفَرْنَا بِكُمْ وَبَدَا بَيْنَنَا
وَبَيْنَكُمُ ٱلْعَدَٰوَةُ وَٱلْبَغْضَآءُ أَبَدًا حَتَّىٰ تُؤْمِنُواْ بِٱللَّهِ وَحْدَهُۥٓ ۚ إِلَّا قَوْلَ
إِبْرَٰهِيمَ لِأَبِيهِ لَأَسْتَغْفِرَنَّ لَكَ وَمَآ أَمْلِكُ لَكَ مِنَ ٱللَّهِ مِن شَىْءٍ ۖ
رَّبَّنَا عَلَيْكَ تَوَكَّلْنَا وَإِلَيْكَ أَنَبْنَا وَإِلَيْكَ ٱلْمَصِيرُ ﴿٤﴾ رَبَّنَا لَا تَجْعَلْنَا
فِتْنَةً لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ وَٱغْفِرْ لَنَا رَبَّنَآ ۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٥﴾

Sura Mumtahana

(1) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku riƙi maƙiyana kuma maƙiyanku masoya, kuna nuna musu soyayya, alhali kuwa sun kafirce wa abin da ya zo muku na gaskiya, suna fitar da Manzo har da ku kanku don kun yi imani da Allah Ubangijinku, idan har kun zamanto kun fito don yin jihadi saboda Ni da kuma neman yardata. Kuna ɓoye ƙaunarku gare su, alhali kuwa Ina sane da abin da kuka ɓoye da kuma abin da kuka bayyana. Duk kuwa wanda ya aikata haka daga cikinku, to haƙiƙa ya ɓace wa hanya madaidaiciya

(2) Idan suka samu nasara a kanku za su zama abokan gabanku, kuma za su miƙa hannayensu da harsunansu zuwa gare ku don munanawa, sun kuma yi burin ina ma da za ku kafirta

(3) Danginku da 'ya'yanku ba za su amfana muku komai ba. A ranar alƙiyama kuma za a yi hukunci a tsakaninku da su. Kuma Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne

(4) Haƙiƙa kyakkyawan abin koyi ya kasance a gare ku game da Ibrahimu da waɗanda suke tare da shi, lokacin da suka ce da mutanensu: "Lalle mu ba ruwanmu da ku, har ma da abin da kuke bauta wa ba Allah ba, mun kafirce muku, kuma gaba da ƙiyayya sun bayyana a tsakaninmu da ku har abada, har sai kun yi imani da Allah Shi kaɗai, in ban da faɗar Ibrahimu ga babansa cewa: 'Lalle zan nema maka gafara, ba na kuma amfana maka komai game da (sakamakon) Allah'; ya Ubangijinmu gare Ka muka dogara, kuma zuwa wurinka muka mayar da lamuranmu, kuma makoma zuwa gare Ka ne

(5) "Ya Ubangijinmu, kada Ka sanya mu fitina ga waɗanda suka kafirta, Ka kuma gafarta mana ya Ubangijinmu; lalle Kai ne Mabuwayi, Mai hikima."

لَقَدْ كَانَ لَكُمْ فِيهِمْ أُسْوَةٌ حَسَنَةٌ لِّمَن كَانَ يَرْجُو اللَّهَ وَالْيَوْمَ الْآخِرَ ۚ
وَمَن يَتَوَلَّ فَإِنَّ اللَّهَ هُوَ الْغَنِيُّ الْحَمِيدُ ﴿٦﴾ عَسَى اللَّهُ أَن يَجْعَلَ بَيْنَكُمْ
وَبَيْنَ الَّذِينَ عَادَيْتُم مِّنْهُم مَّوَدَّةً ۚ وَاللَّهُ قَدِيرٌ ۚ وَاللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ
﴿٧﴾ لَّا يَنْهَاكُمُ اللَّهُ عَنِ الَّذِينَ لَمْ يُقَاتِلُوكُمْ فِي الدِّينِ وَلَمْ يُخْرِجُوكُم
مِّن دِيَارِكُمْ أَن تَبَرُّوهُمْ وَتُقْسِطُوا إِلَيْهِمْ ۚ إِنَّ اللَّهَ يُحِبُّ الْمُقْسِطِينَ
﴿٨﴾ إِنَّمَا يَنْهَاكُمُ اللَّهُ عَنِ الَّذِينَ قَاتَلُوكُمْ فِي الدِّينِ وَأَخْرَجُوكُم مِّن
دِيَارِكُمْ وَظَاهَرُوا عَلَىٰ إِخْرَاجِكُمْ أَن تَوَلَّوْهُمْ ۚ وَمَن يَتَوَلَّهُمْ فَأُولَٰئِكَ
هُمُ الظَّالِمُونَ ﴿٩﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا إِذَا جَاءَكُمُ الْمُؤْمِنَاتُ مُهَاجِرَاتٍ
فَامْتَحِنُوهُنَّ ۖ اللَّهُ أَعْلَمُ بِإِيمَانِهِنَّ ۖ فَإِنْ عَلِمْتُمُوهُنَّ مُؤْمِنَاتٍ فَلَا
تَرْجِعُوهُنَّ إِلَى الْكُفَّارِ ۖ لَا هُنَّ حِلٌّ لَّهُمْ وَلَا هُمْ يَحِلُّونَ لَهُنَّ ۖ وَآتُوهُم
مَّا أَنفَقُوا ۚ وَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ أَن تَنكِحُوهُنَّ إِذَا آتَيْتُمُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ ۚ
وَلَا تُمْسِكُوا بِعِصَمِ الْكَوَافِرِ وَاسْأَلُوا مَا أَنفَقْتُمْ وَلْيَسْأَلُوا مَا أَنفَقُوا ۚ
ذَٰلِكُمْ حُكْمُ اللَّهِ يَحْكُمُ بَيْنَكُمْ ۖ وَاللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿١٠﴾ وَإِن فَاتَكُمْ
شَيْءٌ مِّنْ أَزْوَاجِكُمْ إِلَى الْكُفَّارِ فَعَاقَبْتُمْ فَآتُوا الَّذِينَ ذَهَبَتْ
أَزْوَاجُهُم مِّثْلَ مَا أَنفَقُوا ۚ وَاتَّقُوا اللَّهَ الَّذِي أَنتُم بِهِ مُؤْمِنُونَ ﴿١١﴾

(6) Hakika abin koyi kyakkyawa ya kasance a gare ku game da su, ga duk wanda ya kasance yana kyakkyawan fatar haduwa da Allah da ranar lahira. Duk kuma wanda ya ba da baya, to lalle Allah Shi ne Mawadaci, Sha-Yabo

(7) Zai yiwu Allah Ya sanya kauna tsakaninku da wadanda kuka yi gaba da su. Allah kuwa Mai ikon (yin haka) ne. Allah kuma Mai gafara ne Mai jin kai

(8) Allah bai hana ku ba game da wadanda ba su yake ku don addini ba, ba su kuma fitar da ku daga gidajenku ba, kan ku kyautata musu, ku kuma yi musu adalci. Lalle Allah Yana son masu adalci

(9) Allah kawai Yana hana ku ne a kan ku kaunaci wadanda suka yake ku don addini, suka kuma fitar da ku daga gidajenku, suka kuma taimaka a kan fitar da ku. Duk kuwa wanda ya kaunace su, to wadannan su ne azzalumai

(10) Ya ku wadanda suka yi imani, idan muminai mata sun zo muku suna masu yin hijira, sai ku jarraba su; Allah ne Ya fi sanin imaninsu; to idan kuka san cewa su muminai ne, to kada ku mayar da su wurin kafirai; su ba halal ba ne gare su (kafirai), su ma (kafiran) ba halal ba ne a gare su; kuma ku ba su abin da suka kashe. Kuma babu laifi a kanku ku aure su idan kun ba su sadakinsu. Kada kuma ku rike igiyar auren mata kafirai, ku tambayi abin da kuka kashe, su ma su tambayi abin da suka kashe[1]. Wannan shi ne hukuncin Allah da Yake hukuntawa a tsakaninku. Allah kuma Masani ne, Mai hikima

(11) Idan wasu matanku sun guje muku zuwa ga kafirai, sai kuka yi yaki kuka samu galaba, to ku bai wa wadanda matansu suka guje musu kamar abin da suka kashe[2]. Ku kuma ku kiyaye dokokin Allah wanda kuke imani da Shi

(1) Watau duk matan da suka yi ridda suka gudu zuwa wajen kafirai, to Musulmi su nemi kafiran su biya su abin da suka kashe wajen auren su. Su ma kafiran su nemi Musulmi su biya su sadakin matansu da suka musulunta suka gudo wajen Musulmi.

(2) Watau daga ganimar da aka samu ta yaki.

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ إِذَا جَآءَكَ ٱلْمُؤْمِنَٰتُ يُبَايِعْنَكَ عَلَىٰٓ أَن لَّا يُشْرِكْنَ بِٱللَّهِ
شَيْـًٔا وَلَا يَسْرِقْنَ وَلَا يَزْنِينَ وَلَا يَقْتُلْنَ أَوْلَٰدَهُنَّ وَلَا يَأْتِينَ
بِبُهْتَٰنٍ يَفْتَرِينَهُۥ بَيْنَ أَيْدِيهِنَّ وَأَرْجُلِهِنَّ وَلَا يَعْصِينَكَ فِى
مَعْرُوفٍ فَبَايِعْهُنَّ وَٱسْتَغْفِرْ لَهُنَّ ٱللَّهَ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ
﴿١٢﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَتَوَلَّوْا۟ قَوْمًا غَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمْ قَدْ
يَئِسُوا۟ مِنَ ٱلْءَاخِرَةِ كَمَا يَئِسَ ٱلْكُفَّارُ مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلْقُبُورِ ﴿١٣﴾

سُورَةُ الصَّفِّ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۖ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ
﴿١﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لِمَ تَقُولُونَ مَا لَا تَفْعَلُونَ ﴿٢﴾
كَبُرَ مَقْتًا عِندَ ٱللَّهِ أَن تَقُولُوا۟ مَا لَا تَفْعَلُونَ ﴿٣﴾ إِنَّ
ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلَّذِينَ يُقَٰتِلُونَ فِى سَبِيلِهِۦ صَفًّا كَأَنَّهُم
بُنْيَٰنٌ مَّرْصُوصٌ ﴿٤﴾ وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦ يَٰقَوْمِ لِمَ
تُؤْذُونَنِى وَقَد تَّعْلَمُونَ أَنِّى رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيْكُمْ ۖ فَلَمَّا زَاغُوٓا۟
أَزَاغَ ٱللَّهُ قُلُوبَهُمْ ۚ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْفَٰسِقِينَ ﴿٥﴾

(12) Ya kai wannan Annabi, idan muminai mata suka zo maka suna yi maka mubaya'a a kan ba za su yi shirka da Allah ba, kuma ba za su yi sata ba, ba kuma za su yi zina ba, kuma ba za su kashe 'ya'yansu ba, kuma ba za su zo da wani ƙage ba wanda za su ƙirƙira (game da ɗan da suka haifa) a tsakanin hannayensu da ƙafafuwansu[1], kuma ba za su saɓa maka ba game da wani aiki na kirki, to sai ka yi musu mubaya'a, ka kuma nema musu gafarar Allah. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(13) Ya ku waɗanda kuka yi imani, kada ku jiɓinci mutanen da Allah ya yi fushi da su[2], haƙiƙa sun ɗebe ƙauna daga lahira kamar yadda kafirai suka ɗebe ƙauna daga na ƙabarurruka[3]

Sura Saff

(1) Duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa ya yi tasbihi ga Allah; Shi kuma Mabuwayi ne, Mai hikima

(2) Ya ku waɗanda suka yi imani, don me kuke faɗar abin da ba kwa aikatawa?

(3) Ya isa babban abin ƙi a wurin Allah, ku riƙa faɗin abin da ba kwa aikatawa

(4) Lalle Allah Yana son waɗanda suke yin yaƙi dominsa sahu-sahu kai ka ce su gini ne wanda yake ɗamfare da juna

(5) Kuma (ka tuna) lokacin da Musa ya ce da mutanensa: "Ya ku mutanena, don me kuke cuta ta, alhali kuma kun san cewa lalle ni Manzon Allah ne zuwa gare ku?" To lokacin da suka kauce sai Allah ya kautar da zukatansu. Allah kuma ba ya shiryar da mutane fasiƙai

(1) Kamar yadda suke yi a jahiliyya idan mace ta yi zina da mazaje da yawa sai ta zaɓi ɗaya ta danganta masa ɗan da ta haifa.

(2) Su ne Yahudawan, waɗanda saboda yawan saɓonsu da kafircinsu har Allah ya yi fushi da su.

(3) Watau bayan an nuna musu makomarsu a wutar jahannama suka fitar da tsammanin samun kuɓuta a ranar alƙiyama.

وَإِذْ قَالَ عِيسَى ٱبْنُ مَرْيَمَ يَٰبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ إِنِّى رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيْكُم مُّصَدِّقًا لِّمَا
بَيْنَ يَدَىَّ مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ وَمُبَشِّرًۢا بِرَسُولٍ يَأْتِى مِنۢ بَعْدِى ٱسْمُهُۥٓ أَحْمَدُ ۖ فَلَمَّا
جَآءَهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ قَالُوا۟ هَٰذَا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿٦﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى
ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ وَهُوَ يُدْعَىٰٓ إِلَى ٱلْإِسْلَٰمِ ۚ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ
﴿٧﴾ يُرِيدُونَ لِيُطْفِـُٔوا۟ نُورَ ٱللَّهِ بِأَفْوَٰهِهِمْ وَٱللَّهُ مُتِمُّ نُورِهِۦ وَلَوْ كَرِهَ
ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿٨﴾ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلْهُدَىٰ وَدِينِ ٱلْحَقِّ لِيُظْهِرَهُۥ
عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْمُشْرِكُونَ ﴿٩﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ هَلْ أَدُلُّكُمْ عَلَىٰ
تِجَٰرَةٍ تُنجِيكُم مِّنْ عَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿١٠﴾ تُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَتُجَٰهِدُونَ
فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمْوَٰلِكُمْ وَأَنفُسِكُمْ ۚ ذَٰلِكُمْ خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿١١﴾
يَغْفِرْ لَكُمْ ذُنُوبَكُمْ وَيُدْخِلْكُمْ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ وَمَسَٰكِنَ
طَيِّبَةً فِى جَنَّٰتِ عَدْنٍ ۚ ذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿١٢﴾ وَأُخْرَىٰ تُحِبُّونَهَا ۖ نَصْرٌ
مِّنَ ٱللَّهِ وَفَتْحٌ قَرِيبٌ ۗ وَبَشِّرِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١٣﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ كُونُوٓا۟
أَنصَارَ ٱللَّهِ كَمَا قَالَ عِيسَى ٱبْنُ مَرْيَمَ لِلْحَوَارِيِّۦنَ مَنْ أَنصَارِىٓ إِلَى ٱللَّهِ ۖ
قَالَ ٱلْحَوَارِيُّونَ نَحْنُ أَنصَارُ ٱللَّهِ ۖ فَـَٔامَنَت طَّآئِفَةٌ مِّنۢ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ
وَكَفَرَت طَّآئِفَةٌ ۖ فَأَيَّدْنَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ عَلَىٰ عَدُوِّهِمْ فَأَصْبَحُوا۟ ظَٰهِرِينَ ﴿١٤﴾

(6) Kuma (ka tuna) lokacin da Isa ɗan Maryamu ya ce: "Ya ku 'ya'yan Isra'ila, lalle ni Manzon Allah ne zuwa gare ku, mai gaskata abin da yake gabanina na Attaura, kuma mai albishir da wani manzo da zai zo bayana, sunansa Ahmadu[1]." To lokacin da ya zo musu da (ayoyi) bayyanannu sai suka ce: "Wannan sihiri ne mabayyani."

(7) Ba wanda kuma ya fi zalunci kamar wanda ya ƙaga wa Allah ƙarya, alhali kuwa shi ana kiran sa zuwa Musulunci. Allah kuma ba Ya shiryar da mutane azzalumai

(8) Suna nufin su dusashe hasken Allah da bakunansu, Allah kuwa Mai cika haskensa ne ko da kafirai sun ƙi

(9) Shi ne Wanda Ya aiko Manzonsa da shiriya da kuma addinin gaskiya don Ya ɗora shi a kan kowane addini, ko da kuwa mushirikai sun ƙi

(10) Ya ku waɗanda suka yi imani, yanzu ba Na nuna muku ku wani ciniki da zai tserar da ku daga azaba mai raɗaɗi ba?

(11) (Shi ne) ku yi imani da Allah da Manzonsa ku kuma yi jihadi don Allah da dukiyoyinku da rayukanku. Wannan shi ne ya fiye muku alheri, idan kun kasance kuna sane (da haka)

(12) (Idan kun yi haka) zai gafarta muku zunubanku Ya kuma shigar da ku gidajen Aljanna (waɗanda) ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu da kuma wuraren zama masu kyau, a cikin gidajen Aljanna na dawwama. Wannan shi ne babban rabo

(13) Da kuma wata ɗayar da kuke so; (watau) nasara daga Allah da kuma buɗi a kusa. Ka kuma yi wa muminai albishir

(14) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku zama masu taimaka wa (addinin) Allah, kamar yadda Isa ɗan Maryamu ya ce da Hawariyawa[2]: "Su wane ne masu taimaka mini zuwa ga Allah?" Hawariyawan suka ce: "Mu ne masu taimaka wa Allah." Sai wata ƙungiya daga Bani Isra'ila suka yi imani, wata ƙungiya kuma ta kafirta, sai Muka ƙarfafa waɗanda suka yi imani a kan maƙiyansu, sai suka wayi gari suna masu cin nasara

(1) Ahmad, ɗaya ne daga cikin sunayen Annabi Muhammad ( ).

(2) Su ne almajiransa da suka yi imani da shi.

سُورَةُ الجُمُعَةِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

يُسَبِّحُ لِلَّهِ مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ الْمَلِكِ الْقُدُّوسِ الْعَزِيزِ
الْحَكِيمِ ﴿١﴾ هُوَ الَّذِي بَعَثَ فِي الْأُمِّيِّينَ رَسُولًا مِّنْهُمْ يَتْلُوا عَلَيْهِمْ
آيَاتِهِ وَيُزَكِّيهِمْ وَيُعَلِّمُهُمُ الْكِتَابَ وَالْحِكْمَةَ وَإِن كَانُوا
مِن قَبْلُ لَفِي ضَلَالٍ مُّبِينٍ ﴿٢﴾ وَآخَرِينَ مِنْهُمْ لَمَّا يَلْحَقُوا بِهِمْ
وَهُوَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ ﴿٣﴾ ذَٰلِكَ فَضْلُ اللَّهِ يُؤْتِيهِ مَن يَشَاءُ وَاللَّهُ
ذُو الْفَضْلِ الْعَظِيمِ ﴿٤﴾ مَثَلُ الَّذِينَ حُمِّلُوا التَّوْرَاةَ ثُمَّ لَمْ
يَحْمِلُوهَا كَمَثَلِ الْحِمَارِ يَحْمِلُ أَسْفَارًا ۚ بِئْسَ مَثَلُ الْقَوْمِ
الَّذِينَ كَذَّبُوا بِآيَاتِ اللَّهِ ۚ وَاللَّهُ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الظَّالِمِينَ
﴿٥﴾ قُلْ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ هَادُوا إِن زَعَمْتُمْ أَنَّكُمْ أَوْلِيَاءُ لِلَّهِ مِن
دُونِ النَّاسِ فَتَمَنَّوُا الْمَوْتَ إِن كُنتُمْ صَادِقِينَ ﴿٦﴾ وَلَا يَتَمَنَّوْنَهُ
أَبَدًا بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ ۗ وَاللَّهُ عَلِيمٌ بِالظَّالِمِينَ ﴿٧﴾ قُلْ
إِنَّ الْمَوْتَ الَّذِي تَفِرُّونَ مِنْهُ فَإِنَّهُ مُلَاقِيكُمْ ۖ ثُمَّ تُرَدُّونَ
إِلَىٰ عَالِمِ الْغَيْبِ وَالشَّهَادَةِ فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٨﴾

Sura Jumu'a

(1) Duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa yana yin tasbihi ga Allah Sarki, Tsarkakakke, Mabuwayi, Mai hikima
(2) Shi ne wanda Ya aiko wa (Larabawa) ummiyyai (watau waɗanda ba sa karatu da rubutu) Manzo daga cikinsu, yana karanta musu ayoyinsa, yana kuma tsarkake su, kuma yana sanar da su Alƙur'ani da hikima, ko da yake a da can sun kasance cikin ɓata mabayyani
(3) Da kuma wasunsu (waɗanda) tukuna ba su riske su ba[1]. Shi ne kuwa Mabuwayi, Mai hikima
(4) Wannan falala ce daga Allah, Yana bayar da ita ga wanda Ya ga dama. Allah kuwa Ma'abocin babbar falala ne
(5) Misalin waɗanda aka ɗora wa Attaura[2] sannan ba su ɗauke ta ba, kamar misalin jaki ne da yake ɗauke da wagagen littattafai. Misalin mutanen da suka ƙaryata ayoyin Allah ya munana. Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane azzalumai
(6) Ka ce: "Ya ku waɗanda suka zama Yahudawa, idan kun riya cewa ku ne masoyan Allah ban da sauran mutane, to ku yi burin mutuwa, idan kun kasance masu gaskiya ne."
(7) Ba za su yi burin ta ba har abada saboda abin da hannayensu suka gabatar. Allah kuwa Masanin azzalumai ne
(8) Ka ce (da su): "Lalle ita mutuwar da kuke gudun ta, lalle za ta haɗu da ku; sannan za a mayar da ku wurin Masanin ɓoye da sarari, sannan Ya ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa."

(1) Watau wasu al'ummu daban waɗanda su ma saƙon zai kai gare su nan gaba.

(2) Su ne malaman Yahudawa da Allah ya sanar da su Attaura; ya umarce su su yi aiki da ita.

(9) Ya ku waɗanda suka yi imani, idan aka kira salla ranar Juma'a[1] sai ku tafi zuwa zikirin Allah, kuma ku bar ciniki. Wannan (shi) ya fi muku alheri, idan kun kasance kuna sane (da haka)
(10) Sannan idan aka gama salla sai ku bazu a bayan ƙasa ku kuma nema daga falalar Allah, kuma ku ambaci Allah da yawa don ku rabauta
(11) Idan kuma suka ga kasuwanci ko wasa sai su watse zuwa gare su, su bar ka a tsaye (kana huɗuba). Ka ce: "Abin da yake wurin Allah ya fi wasa da ciniki. Kuma Allah Fiyayyen masu arzutawa ne."

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا نُودِىَ لِلصَّلَوٰةِ مِن يَوۡمِ ٱلۡجُمُعَةِ فَٱسۡعَوۡاْ
إِلَىٰ ذِكۡرِ ٱللَّهِ وَذَرُواْ ٱلۡبَيۡعَۚ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ
٩ فَإِذَا قُضِيَتِ ٱلصَّلَوٰةُ فَٱنتَشِرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَٱبۡتَغُواْ
مِن فَضۡلِ ٱللَّهِ وَٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ كَثِيرٗا لَّعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ١٠
وَإِذَا رَأَوۡاْ تِجَٰرَةً أَوۡ لَهۡوًا ٱنفَضُّوٓاْ إِلَيۡهَا وَتَرَكُوكَ قَآئِمٗاۚ قُلۡ مَا عِندَ
ٱللَّهِ خَيۡرٞ مِّنَ ٱللَّهۡوِ وَمِنَ ٱلتِّجَٰرَةِۚ وَٱللَّهُ خَيۡرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ١١

سُورَةُ المُنَافِقُونَ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِذَا جَآءَكَ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ قَالُواْ نَشۡهَدُ إِنَّكَ لَرَسُولُ ٱللَّهِۘ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ إِنَّكَ
لَرَسُولُهُۥۖ وَٱللَّهُ يَشۡهَدُ إِنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ لَكَٰذِبُونَ ١ ٱتَّخَذُوٓاْ
أَيۡمَٰنَهُمۡ جُنَّةٗ فَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِۚ إِنَّهُمۡ سَآءَ مَا كَانُواْ
يَعۡمَلُونَ ٢ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ ءَامَنُواْ ثُمَّ كَفَرُواْ فَطُبِعَ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ فَهُمۡ
لَا يَفۡقَهُونَ ٣ ۞ وَإِذَا رَأَيۡتَهُمۡ تُعۡجِبُكَ أَجۡسَامُهُمۡۖ وَإِن يَقُولُواْ
تَسۡمَعۡ لِقَوۡلِهِمۡۖ كَأَنَّهُمۡ خُشُبٞ مُّسَنَّدَةٞۖ يَحۡسَبُونَ كُلَّ صَيۡحَةٍ
عَلَيۡهِمۡۚ هُمُ ٱلۡعَدُوُّ فَٱحۡذَرۡهُمۡۚ قَٰتَلَهُمُ ٱللَّهُۖ أَنَّىٰ يُؤۡفَكُونَ ٤

Sura Munafikun

(1) Idan munafukai suka zo maka sai suka ce: "Muna shaidawa cewa lalle kai Manzon Allah ne." Allah kuma Yana sane da cewa kai tabbas Manzonsa ne, kuma Allah Yana shaidawa cewa munafukai tabbas ƙarya suke yi
(2) Sun ɗauki rantse-rantsensu garkuwa, saboda haka suka kange (mutane) daga hanyar Allah. Lalle su abin da suka kasance suna aikatawa ya munana
(3) Wannan kuwa saboda cewa sun yi imani sannan suka kafirta, sai aka rufe zukatansu, saboda haka su ba sa fahimta
(4) Idan ka gan su sai jikkunansu su ƙayatar da kai; idan kuma suka yi magana za ka saurari maganarsu; kai ka ce su wasu gumaguman itatuwa ne a jingine[2]; suna tsammanin kowace irin kururuwa saboda su ne. Su ne maƙiya, saboda haka ka yi hattara da su. Allah kuma Ya la'ance su; ta ina ne ake karkatar da su?

(1) Watau kiran salla bayan liman ya hau kan mimbari. Wajibi a lokacin duk wani Musulmi ya bar duk wata sabga ta saye da sayarwa.

(2) Watau dai wannan cika fuskar duka fankanfayau ne, ba sa fahimtar komai daga bayanan da Annabi ( ) yake yi.

وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ تَعَالَوْا۟ يَسْتَغْفِرْ لَكُمْ رَسُولُ ٱللَّهِ لَوَّوْا۟ رُءُوسَهُمْ
وَرَأَيْتَهُمْ يَصُدُّونَ وَهُم مُّسْتَكْبِرُونَ ۝٥ سَوَآءٌ عَلَيْهِمْ
أَسْتَغْفَرْتَ لَهُمْ أَمْ لَمْ تَسْتَغْفِرْ لَهُمْ لَن يَغْفِرَ ٱللَّهُ لَهُمْ ۚ
إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْفَٰسِقِينَ ۝٦ هُمُ ٱلَّذِينَ يَقُولُونَ
لَا تُنفِقُوا۟ عَلَىٰ مَنْ عِندَ رَسُولِ ٱللَّهِ حَتَّىٰ يَنفَضُّوا۟ ۗ وَلِلَّهِ
خَزَآئِنُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَلَٰكِنَّ ٱلْمُنَٰفِقِينَ لَا يَفْقَهُونَ
۝٧ يَقُولُونَ لَئِن رَّجَعْنَآ إِلَى ٱلْمَدِينَةِ لَيُخْرِجَنَّ ٱلْأَعَزُّ
مِنْهَا ٱلْأَذَلَّ ۚ وَلِلَّهِ ٱلْعِزَّةُ وَلِرَسُولِهِۦ وَلِلْمُؤْمِنِينَ وَلَٰكِنَّ
ٱلْمُنَٰفِقِينَ لَا يَعْلَمُونَ ۝٨ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تُلْهِكُمْ
أَمْوَٰلُكُمْ وَلَآ أَوْلَٰدُكُمْ عَن ذِكْرِ ٱللَّهِ ۚ وَمَن يَفْعَلْ
ذَٰلِكَ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْخَٰسِرُونَ ۝٩ وَأَنفِقُوا۟ مِن مَّا رَزَقْنَٰكُم
مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِىَ أَحَدَكُمُ ٱلْمَوْتُ فَيَقُولَ رَبِّ لَوْلَآ أَخَّرْتَنِىٓ
إِلَىٰٓ أَجَلٍ قَرِيبٍ فَأَصَّدَّقَ وَأَكُن مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ۝١٠ وَلَن
يُؤَخِّرَ ٱللَّهُ نَفْسًا إِذَا جَآءَ أَجَلُهَا ۚ وَٱللَّهُ خَبِيرٌۢ بِمَا تَعْمَلُونَ ۝١١

سُورَةُ التَّغَابُنِ

(5) Idan kuma aka ce da su: “Ku zo Manzon Allah ya nema muku gafara,” sai su kau da kansu, sai ka gan su suna bijirewa, alhalin suna masu girman kai

(6) Duk daya ne game da su, ka nema musu gafara, ko ba ka nema musu gafara ba, Allah ba zai gafarta musu ba har abada. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutane fasiƙai

(7) Su ne waɗanda suke cewa: “Kada ku ciyar da waɗanda suke wurin Manzon Allah har sai sun dare[1]”. Alhali kuwa taskokin sammai da ƙasa na Allah ne, sai dai kuma munafukai ba sa ganewa

(8) Suna cewa: “Tabbas idan muka koma Madina, lalle mafi daraja zai fitar da mafi wulaƙanci daga cikinta[2]”. Alhali kuwa girma na Allah ne da Manzonsa da kuma muminai, sai dai kuma munafukai ba sa sanin (haka)

(9) Ya ku waɗanda suka yi imani, kada dukiyoyinku da ‘ya’yanku su shagaltar da ku daga ambaton Allah[3]. Duk wanda ya aikata haka kuwa, to waɗannan su ne taɓaɓɓu

(10) Kuma ku ciyar daga abin da Muka arzuta ku tun kafin mutuwa ta zo wa ɗayanku sannan ya riƙa cewa: “Ya Ubangijina, me ya hana Ka saurara min zuwa wani ɗan lokaci na kusa sai in ba da gaskiya in kuma zama cikin bayi nagari.”

(11) Allah kuwa ba zai taɓa saurara wa wani rai ba idan ajalinsa ya zo. Allah kuwa Masanin abin da kuke aikatawa ne

(1) Watau su daina taimaka wa sahabbai faƙirai da suke tare da Manzon Allah ( ) har sai sun waste sun bar shi.

(2) Watau shugaban munafukai na Madina Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salul shi ne yake faɗa wa Annabi ( ) wannan mummunar maganar.

(3) Watau su ɗauke muku hankali daga salla da sauran farillan Musulunci da zikirin Allah.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يُسَبِّحُ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلْأَرْضِ ۖ لَهُ ٱلْمُلْكُ وَلَهُ ٱلْحَمْدُ ۖ
وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿١﴾ هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَكُمْ فَمِنكُمْ كَافِرٌ وَمِنكُم
مُّؤْمِنٌ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿٢﴾ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ
بِٱلْحَقِّ وَصَوَّرَكُمْ فَأَحْسَنَ صُوَرَكُمْ ۖ وَإِلَيْهِ ٱلْمَصِيرُ ﴿٣﴾ يَعْلَمُ
مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَيَعْلَمُ مَا تُسِرُّونَ وَمَا تُعْلِنُونَ ۚ وَٱللَّهُ
عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿٤﴾ أَلَمْ يَأْتِكُمْ نَبَؤُا۟ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِن قَبْلُ
فَذَاقُوا۟ وَبَالَ أَمْرِهِمْ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٥﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُۥ كَانَت تَّأْتِيهِمْ
رُسُلُهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَقَالُوٓا۟ أَبَشَرٌ يَهْدُونَنَا فَكَفَرُوا۟ وَتَوَلَّوا۟ ۖ وَّٱسْتَغْنَى
ٱللَّهُ ۚ وَٱللَّهُ غَنِىٌّ حَمِيدٌ ﴿٦﴾ زَعَمَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ أَن لَّن يُبْعَثُوا۟ ۚ قُلْ بَلَىٰ
وَرَبِّى لَتُبْعَثُنَّ ثُمَّ لَتُنَبَّؤُنَّ بِمَا عَمِلْتُمْ ۚ وَذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ ﴿٧﴾
فَـَٔامِنُوا۟ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَٱلنُّورِ ٱلَّذِىٓ أَنزَلْنَا ۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ
﴿٨﴾ يَوْمَ يَجْمَعُكُمْ لِيَوْمِ ٱلْجَمْعِ ۖ ذَٰلِكَ يَوْمُ ٱلتَّغَابُنِ ۗ وَمَن يُؤْمِنۢ بِٱللَّهِ
وَيَعْمَلْ صَٰلِحًا يُكَفِّرْ عَنْهُ سَيِّـَٔاتِهِۦ وَيُدْخِلْهُ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن
تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۚ ذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿٩﴾

Sura Taghabun

(1) Abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa yana tasbihi ga Allah; mulki nasa ne kuma yabo ya tabbata a gare Shi; kuma Shi Mai iko ne a kan komai

(2) Shi ne Wanda Ya halicce ku, don haka daga cikinku akwai kafiri, daga cikinku kuma akwai mumini. Allah kuwa Mai ganin abin da kuke aikatawa ne

(3) Ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya, kuma Ya suranta ku, sannan Ya kyautata surorinku; zuwa gare Shi ne kuma makomarku take

(4) Yana sane da abin da yake cikin sammai da ƙasa, kuma Yana sane da abin da kuke ɓoyewa da abin da kuke bayyanawa. Allah kuma Masanin abubuwan da suke cikin zukata ne

(5) Yanzu labarin waɗanda suka kafirta gabaninku bai zo muku ba? Ai sun ɗanɗani uƙubar kafircinsu (a duniya), suna kuma da azaba mai raɗaɗi (a lahira)

(6) Wannan kuwa saboda lalle manzanninsu sun kasance suna zuwa musu da ayoyi bayyanannu, sai suka ce: "Yanzu mutane ne za su shiryar da mu?" Saboda haka suka kafirce suka kuma ba da baya, Allah kuma Ya wadatu. Allah kuma Mawadaci ne Sha-yabo

(7) Waɗanda suka kafirta sun riya cewa ba za a tashe su ba har abada. Ka ce: "A'a, na rantse da Ubangijina tabbas za a tashe ku, sannan kuma tabbas za a ba ku labarin abin da kuka aikata. Wannan kuwa mai sauƙi ne a wurin Allah

(8) "To ku yi imani da Allah da Manzonsa da kuma hasken da Muka saukar (watau Alƙur'ani). Allah kuma Masanin abin da kuke aikatawa ne

(9) "A ranar da zai tara ku a ranar taruwa; wannan kuwa ita ce ranar kamunga[1]. Duk kuwa wanda ya yi imani da Allah ya kuma yi aiki nagari zai kankare masa zunubansa, Ya kuma shigar da shi gidajen Aljanna (waɗanda) ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu har abada. Wannan shi ne babban rabo."

(1) Watau ranar da za su ga asara ta bayyana a gare su a fili, inda muminai za su gaje gidajen kafirai a Aljanna, su kuma kafirai su gaje gidajen 'yan Aljanna a wuta.

وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِ
خَٰلِدِينَ فِيهَاۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ١٠ مَآ أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٍ
إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۗ وَمَن يُؤۡمِنۢ بِٱللَّهِ يَهۡدِ قَلۡبَهُۥۚ وَٱللَّهُ بِكُلِّ
شَيۡءٍ عَلِيمٞ ١١ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَۚ فَإِن
تَوَلَّيۡتُمۡ فَإِنَّمَا عَلَىٰ رَسُولِنَا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ١٢ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ
إِلَّا هُوَۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ١٣ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّ مِنۡ أَزۡوَٰجِكُمۡ وَأَوۡلَٰدِكُمۡ عَدُوّٗا
لَّكُمۡ فَٱحۡذَرُوهُمۡۚ وَإِن تَعۡفُواْ وَتَصۡفَحُواْ وَتَغۡفِرُواْ
فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٌ ١٤ إِنَّمَآ أَمۡوَٰلُكُمۡ وَأَوۡلَٰدُكُمۡ
فِتۡنَةٞۚ وَٱللَّهُ عِندَهُۥٓ أَجۡرٌ عَظِيمٞ ١٥ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ مَا ٱسۡتَطَعۡتُمۡ
وَٱسۡمَعُواْ وَأَطِيعُواْ وَأَنفِقُواْ خَيۡرٗا لِّأَنفُسِكُمۡۗ وَمَن يُوقَ
شُحَّ نَفۡسِهِۦ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ١٦ إِن تُقۡرِضُواْ
ٱللَّهَ قَرۡضًا حَسَنٗا يُضَٰعِفۡهُ لَكُمۡ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۚ وَٱللَّهُ شَكُورٌ
حَلِيمٌ ١٧ عَٰلِمُ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١٨

سُورَةُ الطَّلَاقِ

(10) Waɗanda kuwa suka kafirce suka ƙaryata ayoyinmu, waɗannan su ne ‘yan wuta, suna masu dawwama a cikinta; makoma kuwa ta munana

(11) Ba wata musiba da ta samu sai da izinin Allah. Duk kuwa wanda ya yi imani da Allah zai shiryi zuciyarsa. Allah kuma Masanin komai ne

(12) Ku bi Allah kuma ku bi Manzon. To idan kuka ba da baya to abin da yake kan Manzonmu kawai shi ne isar da aike

(13) Allah, babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, to sai muminai su dogara ga Allah

kawai

(14) Ya ku waɗanda suka yi imani, lalle wasu daga matanku da ‘ya’yanku maƙiyanku ne[1], sai ku yi hattara da su. Idan kuma kuka yafe kuka kau da kai, to lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(15) Dukiyoyinku da ‘ya’yanku fitina ne kawai (a gare ku). Kuma a wurin Allah lada mai girma yake

(16) Saboda haka ku kiyaye dokokin Allah gwargwadon ikonku, kuma ku yi sauraro, ku bi, ku kuma ciyar, shi ya fi alheri a gare ku. Duk kuwa wanda aka kare shi daga tsananin son kansa, to waɗannan su ne masu babban rabo

(17) Idan kuka ranta wa Allah kyakkyawan rance, to zai ninninka muku shi[2], Ya kuma gafarta muku. Allah kuma Mai godewa ne, Mai haƙuri

(18) Masanin ɓoye da sarari ne, Mabuwayi, Mai hikima

(1) Watau waɗanda suke ƙoƙarin hana su ɗa’ar Allah ko su jefa su cikin saɓon Allah.

(2) Watau duk wani kyakkyawan aiki ɗaya zai ninka musu shi gida goma, har zuwa ninki ɗari bakwai, har zuwa ninkin ba ninkin mai yawa.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ إِذَا طَلَّقْتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَطَلِّقُوهُنَّ لِعِدَّتِهِنَّ وَأَحْصُوا۟ ٱلْعِدَّةَ ۖ
وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ رَبَّكُمْ ۖ لَا تُخْرِجُوهُنَّ مِنۢ بُيُوتِهِنَّ وَلَا يَخْرُجْنَ إِلَّآ أَن
يَأْتِينَ بِفَٰحِشَةٍ مُّبَيِّنَةٍ ۚ وَتِلْكَ حُدُودُ ٱللَّهِ ۚ وَمَن يَتَعَدَّ حُدُودَ ٱللَّهِ
فَقَدْ ظَلَمَ نَفْسَهُۥ ۚ لَا تَدْرِى لَعَلَّ ٱللَّهَ يُحْدِثُ بَعْدَ ذَٰلِكَ أَمْرًا ﴿١﴾
فَإِذَا بَلَغْنَ أَجَلَهُنَّ فَأَمْسِكُوهُنَّ بِمَعْرُوفٍ أَوْ فَارِقُوهُنَّ بِمَعْرُوفٍ
وَأَشْهِدُوا۟ ذَوَىْ عَدْلٍ مِّنكُمْ وَأَقِيمُوا۟ ٱلشَّهَٰدَةَ لِلَّهِ ۚ ذَٰلِكُمْ يُوعَظُ
بِهِۦ مَن كَانَ يُؤْمِنُ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ ۚ وَمَن يَتَّقِ ٱللَّهَ يَجْعَل لَّهُۥ
مَخْرَجًا ﴿٢﴾ وَيَرْزُقْهُ مِنْ حَيْثُ لَا يَحْتَسِبُ ۚ وَمَن يَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِ
فَهُوَ حَسْبُهُۥ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ بَٰلِغُ أَمْرِهِۦ ۚ قَدْ جَعَلَ ٱللَّهُ لِكُلِّ شَىْءٍ
قَدْرًا ﴿٣﴾ وَٱلَّٰٓـِٔى يَئِسْنَ مِنَ ٱلْمَحِيضِ مِن نِّسَآئِكُمْ إِنِ
ٱرْتَبْتُمْ فَعِدَّتُهُنَّ ثَلَٰثَةُ أَشْهُرٍ وَٱلَّٰٓـِٔى لَمْ يَحِضْنَ ۚ وَأُو۟لَٰتُ
ٱلْأَحْمَالِ أَجَلُهُنَّ أَن يَضَعْنَ حَمْلَهُنَّ ۚ وَمَن يَتَّقِ ٱللَّهَ
يَجْعَل لَّهُۥ مِنْ أَمْرِهِۦ يُسْرًا ﴿٤﴾ ذَٰلِكَ أَمْرُ ٱللَّهِ أَنزَلَهُۥٓ إِلَيْكُمْ ۚ
وَمَن يَتَّقِ ٱللَّهَ يُكَفِّرْ عَنْهُ سَيِّـَٔاتِهِۦ وَيُعْظِمْ لَهُۥٓ أَجْرًا ﴿٥﴾

Sura Ɗalaƙ

(1) Ya kai wannan Annabi, (ka ce da jama'arka): "Idan za ku saki mata sai ku sake su a farkon iddarsu[1], kuma ku kula da kiyaye ƙidaya idda[2]; kuma ku kiyaye dokokin Ubangijinku; kada ku fitar da su daga ɗakunansu, su ma kada su fita sai dai idan sun aikata alfasha bayayyananna. Waɗannan kuwa su ne iyakokin Allah. Wanda kuwa duk ya ƙetare iyakokin Allah, to haƙiƙa ya zalunci kansa. Ba ka sani ba ko Allah zai farar da wani al'amari bayan wannan[3]

(2) Idan kuma sun kusa isa ƙarshen iddarsu, to ku riƙe su da kyautatawa (ku yi kome), ko kuma ku rabu da su da kyautatawa, kuma ku kafa shaidar adilai guda biyu daga cikinku, ku kuma tsayar da shaidarku saboda Allah. Wannan shi ne ake yin wa'azi da shi ga wanda ya kasance yana yin imani da Allah da ranar lahira. Wanda kuma ya kiyaye dokokin Allah to zai sanya masa mafita

(3) Ya kuma arzuta shi ta inda ba ya tsammani. Duk wanda kuma ya dogara ga Allah to Shi Ya ishe shi. Lalle Allah Mai zartar da al'amarinsa ne. Haƙiƙa kuma Allah Ya sanya iyaka ga kowane abu

(4) Waɗanda kuma suka ɗebe ƙauna ta yin al'ada daga matanku, idan kun yi kokwanto, to iddarsu wata uku ne, da kuma waɗanda ba su taɓa yin al'ada ba. Mata masu ciki kuma ƙarewar iddarsu ita ce haife cikinsu[1]. Duk kuma wanda ya kiyaye dokokin Allah, to zai sanya masa sauƙi game da al'amarinsa

(5) Wannan shi ne hukuncin Allah da Ya saukar da shi a gare ku. Duk kuma wanda ya kiyaye dokokin Allah, to zai kankare masa zunubbansa Ya kuma girmama masa lada

(1) Watau lokacin da suka yi tsarkin haila wanda kuma ba su sadu da su ba a cikinsa, ko kuma idan ciki ya bayyana.

(2) Domin su iya dawo da matansu kafin ƙarewarta idan suna buƙatar yin haka.

(3) Watau Allah ya sake kawo jituwa a tsakanin mijin da matar su fahimci juna su mayar da aurensu.

(4) Hakanan iddar matar da mijinta ya rasu.

أَسْكِنُوهُنَّ مِنْ حَيْثُ سَكَنتُم مِّن وُجْدِكُمْ وَلَا تُضَآرُّوهُنَّ لِتُضَيِّقُوا۟
عَلَيْهِنَّ ۚ وَإِن كُنَّ أُو۟لَٰتِ حَمْلٍ فَأَنفِقُوا۟ عَلَيْهِنَّ حَتَّىٰ يَضَعْنَ حَمْلَهُنَّ ۚ فَإِنْ
أَرْضَعْنَ لَكُمْ فَـَٔاتُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ ۖ وَأْتَمِرُوا۟ بَيْنَكُم بِمَعْرُوفٍ ۖ وَإِن
تَعَاسَرْتُمْ فَسَتُرْضِعُ لَهُۥٓ أُخْرَىٰ ﴿٦﴾ لِيُنفِقْ ذُو سَعَةٍ مِّن سَعَتِهِۦ ۖ وَمَن
قُدِرَ عَلَيْهِ رِزْقُهُۥ فَلْيُنفِقْ مِمَّآ ءَاتَىٰهُ ٱللَّهُ ۚ لَا يُكَلِّفُ ٱللَّهُ نَفْسًا إِلَّا
مَآ ءَاتَىٰهَا ۚ سَيَجْعَلُ ٱللَّهُ بَعْدَ عُسْرٍ يُسْرًا ﴿٧﴾ وَكَأَيِّن مِّن قَرْيَةٍ عَتَتْ
عَنْ أَمْرِ رَبِّهَا وَرُسُلِهِۦ فَحَاسَبْنَٰهَا حِسَابًا شَدِيدًا وَعَذَّبْنَٰهَا عَذَابًا
نُّكْرًا ﴿٨﴾ فَذَاقَتْ وَبَالَ أَمْرِهَا وَكَانَ عَٰقِبَةُ أَمْرِهَا خُسْرًا ﴿٩﴾ أَعَدَّ ٱللَّهُ
لَهُمْ عَذَابًا شَدِيدًا ۖ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ يَٰٓأُو۟لِى ٱلْأَلْبَٰبِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ۚ قَدْ أَنزَلَ
ٱللَّهُ إِلَيْكُمْ ذِكْرًا ﴿١٠﴾ رَّسُولًا يَتْلُوا۟ عَلَيْكُمْ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ مُبَيِّنَٰتٍ لِّيُخْرِجَ
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ ۚ وَمَن يُؤْمِنۢ
بِٱللَّهِ وَيَعْمَلْ صَٰلِحًا يُدْخِلْهُ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ
فِيهَآ أَبَدًا ۖ قَدْ أَحْسَنَ ٱللَّهُ لَهُۥ رِزْقًا ﴿١١﴾ ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ سَبْعَ سَمَٰوَٰتٍ
وَمِنَ ٱلْأَرْضِ مِثْلَهُنَّ ۖ يَتَنَزَّلُ ٱلْأَمْرُ بَيْنَهُنَّ لِتَعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ
كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ۙ وَأَنَّ ٱللَّهَ قَدْ أَحَاطَ بِكُلِّ شَىْءٍ عِلْمًا ﴿١٢﴾

(6) Ku zaunar da su (matayen) a inda kuka zauna daidai da samunku, kada kuma ku cuce su don ku ƙuntata musu. Idan kuwa sun kasance masu ciki to sai ku ciyar da su har sai sun haife cikinsu. Sannan idan sun shayar muku da (‘ya’yanku) sai ku ba su ladansu; ku kuma daidaita a tsakaninku ta hanya tagari; idan kuma kuka kasa daidaitawa, to wata mai shayarwar sai ta shayar masa

(7) Mawadaci ya ciyar daidai da wadatarsa; wanda kuwa aka ƙuntata masa arzikinsa, to ya ciyar daidai da abin da Allah Ya ba shi. Allah ba Ya ɗora wa rai sai gwargwadon abin da Ya ba shi. Kuma da sannu Allah zai sanya sauƙi bayan tsanani

(8) Alƙaryu da dama sun yi wa Ubangijinsu da manzanninsa taurin kai, sai Muka yi musu hisabi mai tsanani, Muka azabtar da su azaba mummuna

(9) Saboda haka su ɗanɗani ƙarshen al’amarinsu, ƙarshen al’amarin nasu kuma ya zama taƀewa

(10) Allah Ya tanadar musu azaba mai tsanani; saboda haka ku kiyaye dokokin Allah ya ku ma’abota hankula waɗanda suka yi imani. Haƙiƙa Allah Ya saukar muku da tunatarwa

(11) (Shi ne) Manzo da yake karanta muku ayoyin Allah bayyanannu, don ya fitar da waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari daga duffai zuwa haske. Duk kuwa wanda ya yi imani da Allah ya kuma yi aiki nagari to zai shigar da shi gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu suna masu dawwama a cikinsu har abada. (Wanda aka yi wa haka kuwa) haƙiƙa Allah Ya kyautata masa arzikinsa

(12) Allah ne Wanda Ya halicci sammai bakwai, ƙasa ma Ya halicci kwatankwacinsu (watau sammai), umarni yana sauka a tsakaninsu, don ku san cewa, Allah Mai iko ne a kan komai, kuma haƙiƙa Allah iliminsa ya kewaye kowane abu

سُورَةُ التَّحۡرِيمِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ لِمَ تُحَرِّمُ مَآ أَحَلَّ ٱللَّهُ لَكَۖ تَبۡتَغِي مَرۡضَاتَ أَزۡوَٰجِكَۚ وَٱللَّهُ
غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١ قَدۡ فَرَضَ ٱللَّهُ لَكُمۡ تَحِلَّةَ أَيۡمَٰنِكُمۡۚ وَٱللَّهُ مَوۡلَىٰكُمۡۖ وَهُوَ
ٱلۡعَلِيمُ ٱلۡحَكِيمُ ٢ وَإِذۡ أَسَرَّ ٱلنَّبِيُّ إِلَىٰ بَعۡضِ أَزۡوَٰجِهِۦ حَدِيثٗا فَلَمَّا
نَبَّأَتۡ بِهِۦ وَأَظۡهَرَهُ ٱللَّهُ عَلَيۡهِ عَرَّفَ بَعۡضَهُۥ وَأَعۡرَضَ عَنۢ بَعۡضٖۖ فَلَمَّا
نَبَّأَهَا بِهِۦ قَالَتۡ مَنۡ أَنۢبَأَكَ هَٰذَاۖ قَالَ نَبَّأَنِيَ ٱلۡعَلِيمُ ٱلۡخَبِيرُ ٣ إِن
تَتُوبَآ إِلَى ٱللَّهِ فَقَدۡ صَغَتۡ قُلُوبُكُمَاۖ وَإِن تَظَٰهَرَا عَلَيۡهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ
هُوَ مَوۡلَىٰهُ وَجِبۡرِيلُ وَصَٰلِحُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۖ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ بَعۡدَ ذَٰلِكَ
ظَهِيرٌ ٤ عَسَىٰ رَبُّهُۥٓ إِن طَلَّقَكُنَّ أَن يُبۡدِلَهُۥٓ أَزۡوَٰجًا خَيۡرٗا مِّنكُنَّ
مُسۡلِمَٰتٖ مُّؤۡمِنَٰتٖ قَٰنِتَٰتٖ تَٰٓئِبَٰتٍ عَٰبِدَٰتٖ سَٰٓئِحَٰتٖ ثَيِّبَٰتٖ
وَأَبۡكَارٗا ٥ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ وَأَهۡلِيكُمۡ نَارٗا
وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلۡحِجَارَةُ عَلَيۡهَا مَلَٰٓئِكَةٌ غِلَاظٞ شِدَادٞ
لَّا يَعۡصُونَ ٱللَّهَ مَآ أَمَرَهُمۡ وَيَفۡعَلُونَ مَا يُؤۡمَرُونَ ٦ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ لَا تَعۡتَذِرُواْ ٱلۡيَوۡمَۖ إِنَّمَا تُجۡزَوۡنَ مَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٧

Sura Tahrim

(1) Ya kai wannan Annabi, don me kake haramta abin da Allah Ya halatta maka[1]; kana neman yardar matanka. Allah kuwa Mai gafara ne, Mai jin ƙai

(2) Haƙiƙa Allah Ya farlanta muku kaffarar rantse-rantsenku[2]. Allah kuwa (Shi ne) Majiɓincin al'amarinku, Shi ne kuma Masani, Mai hikima

(3) Kuma (ka tuna) lokacin da Annabi ya asirta wani zance ga wata daga matansa[3], to lokacin da ta ba da labarinsa Allah kuma Ya bayyana masa shi, sai ya sanar da (ita) sashinsa ya kuma kawar da kai ga wani sashi; to yayin da ya ba ta labarinsa sai ta ce: "Wane ne ya ba ka labarin wannan?" Sai ya ce: "Masani Mai zuzzurfan ilimi ne Ya ba ni labarinsa."

(4) Idan (ku biyun)[4] kuka tuba zuwa ga Allah, to haƙiƙa zukatanku sun riga sun karkata; idan kuwa kuka haɗe masa kai, to lalle Allah Shi ne Majiɓincin al'amarinsa, da Jibrilu da salihan muminai; mala'iku ma bayan wannan masu taimakawa ne

(5) Tabbas idan ya sake ku Ubangijinsa zai musanya masa wasu matan fiye da ku (su zama) Musulmi, muminai, masu biyayya, masu tuba, masu bautar Allah, masu azumi, zawarawa da 'yanmata

(6) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kare kawunanku da iyalanku daga wuta (wadda) makamashinta mutane ne da duwatsu, masu kula da ita mala'iku ne masu kaushin hali, masu tsananin gaske, ba sa saɓa wa Allah abin da Ya umarce su, suna kuma aikata abin da ake umartar su

(7) Ya ku waɗanda suka kafirta, kada ku kawo wani hanzari a yau; ana saka muku ne kawai da abin da kuka kasance kuna aikatawa

(1) Watau kamar yin sa-ɗaka da kuyangarsa ko shan zuma.

(2) Kamar yadda aka yi bayani a Suratul Ma'ida aya ta 89.

(3) Ita ce Hafsa ( ).

(4) Watau Hafsa da A'isha, Allah ya yarda da su.

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ تُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ تَوۡبَةٗ نَّصُوحًا عَسَىٰ رَبُّكُمۡ
أَن يُكَفِّرَ عَنكُمۡ سَيِّـَٔاتِكُمۡ وَيُدۡخِلَكُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي
مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ يَوۡمَ لَا يُخۡزِي ٱللَّهُ ٱلنَّبِيَّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
مَعَهُۥۖ نُورُهُمۡ يَسۡعَىٰ بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَبِأَيۡمَٰنِهِمۡ يَقُولُونَ رَبَّنَآ
أَتۡمِمۡ لَنَا نُورَنَا وَٱغۡفِرۡ لَنَآۖ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٨
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ جَٰهِدِ ٱلۡكُفَّارَ وَٱلۡمُنَٰفِقِينَ وَٱغۡلُظۡ عَلَيۡهِمۡۚ
وَمَأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ٩ ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلٗا
لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱمۡرَأَتَ نُوحٖ وَٱمۡرَأَتَ لُوطٖۖ كَانَتَا تَحۡتَ
عَبۡدَيۡنِ مِنۡ عِبَادِنَا صَٰلِحَيۡنِ فَخَانَتَاهُمَا فَلَمۡ يُغۡنِيَا عَنۡهُمَا
مِنَ ٱللَّهِ شَيۡـٔٗا وَقِيلَ ٱدۡخُلَا ٱلنَّارَ مَعَ ٱلدَّٰخِلِينَ ١٠
وَضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلٗا لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱمۡرَأَتَ فِرۡعَوۡنَ إِذۡ
قَالَتۡ رَبِّ ٱبۡنِ لِي عِندَكَ بَيۡتٗا فِي ٱلۡجَنَّةِ وَنَجِّنِي مِن فِرۡعَوۡنَ
وَعَمَلِهِۦ وَنَجِّنِي مِنَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ١١ وَمَرۡيَمَ ٱبۡنَتَ
عِمۡرَٰنَ ٱلَّتِيٓ أَحۡصَنَتۡ فَرۡجَهَا فَنَفَخۡنَا فِيهِ مِن رُّوحِنَا
وَصَدَّقَتۡ بِكَلِمَٰتِ رَبِّهَا وَكُتُبِهِۦ وَكَانَتۡ مِنَ ٱلۡقَٰنِتِينَ ١٢

(8) Ya ku waɗanda suka yi imani, ku tuba zuwa ga Allah tuba na gaskiya, tabbas Ubangijinku zai kankare muku kurakuranku Ya kuma shigar da ku gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, a ranar da Allah ba zai kunyata Manzo da waɗanda suka yi imani tare da shi ba; haskensu yana tafe a gabansu da damansu suna cewa: "Ya Ubangijinmu, Ka sa haskenmu ya ɗore, Ka kuma gafarta mana; lalle Kai Mai iko ne a kan komai."

(9) Ya kai wannan Annabi, ka yaƙi kafirai da munafukai, ka kuma tsananta musu.

Makomarsu kuma Jahannama ce; makoma kuwa ta munana

(10) Allah Ya ba da wani misali ga waɗanda suka kafirta da matar Nuhu da matar Luɗu; sun kasance ƙarƙashin (igiyar auren) wasu bayi su biyu salihai daga bayinmu, sai suka ha'ince su[1], saboda haka ba su wadatar musu komai ba (daga azabar) Allah, aka kuma ce: "Ku shiga wuta tare da masu shiga."

(11) Allah kuma Ya ba da wani misali ga waɗanda suka yi imani da matar Fir'auna lokacin da ta ce: "Ya Ubangijina, Ka gina min gida a wurinka cikin Aljanna, Ka kuma tserar da ni daga Fir'auna da aikinsa, kuma Ka tserar da ni daga azzaluman mutane."

(12) Da kuma Maryamu 'yar Imrana wadda ta kiyaye matuncinta, sai Muka masa busa daga Ruhinmu[2], ta kuma gaskata ayoyin Ubangijinta da littattafansa, ta kuma kasance daga masu biyayya ga Allah

(1) Watau suka kafirce musu, suka riƙa hana mutane bin addinin Allah, suka kuma riƙa goyon bayan kafirai.

(2) Watau Allah ya umarci Mala'ika Jibrilu ( ) ya yi busa a gare ta.

سُورَةُ الْمُلْكِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

تَبَارَكَ الَّذِي بِيَدِهِ الْمُلْكُ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿١﴾ الَّذِي خَلَقَ
الْمَوْتَ وَالْحَيَاةَ لِيَبْلُوَكُمْ أَيُّكُمْ أَحْسَنُ عَمَلًا ۚ وَهُوَ الْعَزِيزُ الْغَفُورُ
﴿٢﴾ الَّذِي خَلَقَ سَبْعَ سَمَاوَاتٍ طِبَاقًا ۖ مَّا تَرَىٰ فِي خَلْقِ الرَّحْمَٰنِ مِن
تَفَاوُتٍ ۖ فَارْجِعِ الْبَصَرَ هَلْ تَرَىٰ مِن فُطُورٍ ﴿٣﴾ ثُمَّ ارْجِعِ الْبَصَرَ كَرَّتَيْنِ
يَنقَلِبْ إِلَيْكَ الْبَصَرُ خَاسِئًا وَهُوَ حَسِيرٌ ﴿٤﴾ وَلَقَدْ زَيَّنَّا السَّمَاءَ
الدُّنْيَا بِمَصَابِيحَ وَجَعَلْنَاهَا رُجُومًا لِّلشَّيَاطِينِ ۖ وَأَعْتَدْنَا لَهُمْ عَذَابَ
السَّعِيرِ ﴿٥﴾ وَلِلَّذِينَ كَفَرُوا بِرَبِّهِمْ عَذَابُ جَهَنَّمَ ۖ وَبِئْسَ الْمَصِيرُ
﴿٦﴾ إِذَا أُلْقُوا فِيهَا سَمِعُوا لَهَا شَهِيقًا وَهِيَ تَفُورُ ﴿٧﴾ تَكَادُ تَمَيَّزُ
مِنَ الْغَيْظِ ۖ كُلَّمَا أُلْقِيَ فِيهَا فَوْجٌ سَأَلَهُمْ خَزَنَتُهَا أَلَمْ يَأْتِكُمْ نَذِيرٌ ﴿٨﴾
قَالُوا بَلَىٰ قَدْ جَاءَنَا نَذِيرٌ فَكَذَّبْنَا وَقُلْنَا مَا نَزَّلَ اللَّهُ مِن شَيْءٍ إِنْ أَنتُمْ
إِلَّا فِي ضَلَالٍ كَبِيرٍ ﴿٩﴾ وَقَالُوا لَوْ كُنَّا نَسْمَعُ أَوْ نَعْقِلُ مَا كُنَّا فِي أَصْحَابِ
السَّعِيرِ ﴿١٠﴾ فَاعْتَرَفُوا بِذَنبِهِمْ فَسُحْقًا لِّأَصْحَابِ السَّعِيرِ ﴿١١﴾ إِنَّ
الَّذِينَ يَخْشَوْنَ رَبَّهُم بِالْغَيْبِ لَهُم مَّغْفِرَةٌ وَأَجْرٌ كَبِيرٌ ﴿١٢﴾

Sura Mulk

(1) Wanda mulki yake a hannunsa alhairansa sun yawaita, kuma Shi Mai iko ne a kan komai
(2) Wanda Ya halicci mutuwa da rayuwa don Ya jarraba ku (Ya bayyana) wane ne a cikinku ya fi kyakkyawan aiki? Shi kuma Mabuwayi ne, Mai gafara
(3) Wanda Ya halicci sammai bakwai hawa-hawa; ba za ka ga wata tangarɗa cikin halittar (Allah) Mai rahama ba. Ka maimaita dubanka, shin za ka ga wata tsaga?
(4) Sannan ka sake mayar da gani sau da yawa, ganin zai dawo maka a ƙasƙance, shi kuma yana a dakushe (bai ga wata tsaga ba)
(5) Kuma haƙiƙa Mun ƙawata saman duniya da taurari Muka sanya su kuma ababan jifan shaiɗanu[1]; Muka kuma tanadar musu azabar (wutar) Sa'ira
(6) Waɗanda kuma suka kafirce wa Ubangijinsu suna da azabar Jahannama; makoma kuwa ta munana
(7) Idan aka jefa su a cikinta sai su ji kururuwarta, tana tafarfasa
(8) Tana kusa da ta kekkece saboda tsananin fushi; duk sanda aka jefa wata tawaga a cikinta sai masu tsaron ta su tambaye su: "Shin mai gargaɗi bai zo muku ba?"
(9) Sai su ce, "E, haka ne, haƙiƙa mai gargaɗi ya zo mana, sai muka ƙaryata, muka kuma ce, Allah bai saukar da wani abu ba, ba kwa a kan komai sai ƀata mai girma."
(10) Suka kuma ce: "Da mun kasance muna fahimta ko kuma muna hankalta, to da ba mu kasance cikin 'yan (wutar) Sa'ira ba."
(11) Sai suka amsa laifinsu, sai (a ce da su): "Can dai da 'yan (wutar) Sa'ira."
(12) Lalle waɗanda suke tsoron Ubangijinsu ba tare da suna ganin sa ba, suna da gafara da kuma lada mai girma

(1) Watau jifar shaiɗanu masu ƙoƙarin satar ji su ƙona su.

وَأَسِرُّوا۟ قَوْلَكُمْ أَوِ ٱجْهَرُوا۟ بِهِۦٓ ۖ إِنَّهُۥ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿١٣﴾ أَلَا
يَعْلَمُ مَنْ خَلَقَ وَهُوَ ٱللَّطِيفُ ٱلْخَبِيرُ ﴿١٤﴾ هُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَرْضَ
ذَلُولًا فَٱمْشُوا۟ فِى مَنَاكِبِهَا وَكُلُوا۟ مِن رِّزْقِهِۦ ۖ وَإِلَيْهِ ٱلنُّشُورُ ﴿١٥﴾
ءَأَمِنتُم مَّن فِى ٱلسَّمَآءِ أَن يَخْسِفَ بِكُمُ ٱلْأَرْضَ فَإِذَا هِىَ تَمُورُ ﴿١٦﴾
أَمْ أَمِنتُم مَّن فِى ٱلسَّمَآءِ أَن يُرْسِلَ عَلَيْكُمْ حَاصِبًا ۖ فَسَتَعْلَمُونَ
كَيْفَ نَذِيرِ ﴿١٧﴾ وَلَقَدْ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ فَكَيْفَ كَانَ نَكِيرِ ﴿١٨﴾
أَوَلَمْ يَرَوْا۟ إِلَى ٱلطَّيْرِ فَوْقَهُمْ صَٰٓفَّٰتٍ وَيَقْبِضْنَ ۚ مَا يُمْسِكُهُنَّ إِلَّا
ٱلرَّحْمَٰنُ ۚ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَىْءٍۭ بَصِيرٌ ﴿١٩﴾ أَمَّنْ هَٰذَا ٱلَّذِى هُوَ جُندٌ لَّكُمْ
يَنصُرُكُم مِّن دُونِ ٱلرَّحْمَٰنِ ۚ إِنِ ٱلْكَٰفِرُونَ إِلَّا فِى غُرُورٍ ﴿٢٠﴾ أَمَّنْ هَٰذَا
ٱلَّذِى يَرْزُقُكُمْ إِنْ أَمْسَكَ رِزْقَهُۥ ۚ بَل لَّجُّوا۟ فِى عُتُوٍّ وَنُفُورٍ ﴿٢١﴾ أَفَمَن
يَمْشِى مُكِبًّا عَلَىٰ وَجْهِهِۦٓ أَهْدَىٰٓ أَمَّن يَمْشِى سَوِيًّا عَلَىٰ صِرَٰطٍ
مُّسْتَقِيمٍ ﴿٢٢﴾ قُلْ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَنشَأَكُمْ وَجَعَلَ لَكُمُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ
وَٱلْأَفْـِٔدَةَ ۖ قَلِيلًا مَّا تَشْكُرُونَ ﴿٢٣﴾ قُلْ هُوَ ٱلَّذِى ذَرَأَكُمْ فِى
ٱلْأَرْضِ وَإِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ﴿٢٤﴾ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلْوَعْدُ إِن كُنتُمْ
صَٰدِقِينَ ﴿٢٥﴾ قُلْ إِنَّمَا ٱلْعِلْمُ عِندَ ٱللَّهِ وَإِنَّمَآ أَنَا۠ نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿٢٦﴾

(13) Da ku ɓoye zancenku ko ku bayyana shi, lalle Shi Masanin abin da yake cikin zukata ne
(14) Yanzu wanda ya yi halitta ba zai san ta ba? Shi ne kuma Mai tausasawa Masani
(15) Shi ne wanda Ya sanya muku ƙasa horarriya[1], saboda haka ku yi tafiya a cikin sasanninta kuma ku ci daga arzikinta; makoma kuwa zuwa gare Shi take
(16) Yanzu kun amince cewa wanda Yake sama Ya kifar da ƙasa da ku, sai kawai ku gan ta tana ta tambal-tambal?
(17) Ko kuma kun amince cewa wanda Yake sama Ya aiko muku da guguwa mai tsakwankwani? To da sannu za ku san yadda (sakamakon) gargaɗina zai zama
(18) Haƙiƙa kuma waɗanda suke gabaninku sun ƙaryata, to yaya (sakamakon) nuna ƙin amincewata ya zama?
(19) Shin ba sa ganin tsuntsaye a samansu suna shimfiɗa (fikafikansu) suna kuma rufe su? Ba wanda yake riƙe da su sai (Allah) Mai rahama. Lalle Shi Mai ganin komai ne
(20) Ko kuwa wace runduna ce kuke da ita da za ta taimaka muku ba (Allah) Mai rahama ba? Su dai kafirai ba sa kan komai sai ruɗi
(21) Ko kuwa wane ne zai arzuta ku idan (Allah) Ya riƙe arzikinsa? A'a, kawai dai sun yi zurfi ne cikin taurin kai da fandarewa
(22) Shin wanda yake tafiya a kife a kan fuskarsa shi ya fi zama a kan daidai ko kuma wanda yake tafiya a miƙe kan hanya madaidaiciya?
(23) Ka ce: "Shi ne (Allah) Wanda Ya fare ku Ya kuma sanya muku ji da gani da zukata; kaɗan ne kawai kuke godewa."
(24) Ka ce: "Shi ne wanda Ya halicce ku a kan ƙasa, kuma zuwa gare Shi za a tattara ku."
(25) Suna kuma cewa: "Yaushe ne wannan alƙawarin, idan kun kasance masu gaskiya?"
(26) Ka ce: "Saninsa yana wurin Allah kawai, kuma ni kawai mai gargaɗi ne mai bayyana (gargaɗin)."

(1) Watau ta zamanto mai sauƙin zama da rayuwa a kanta, ba tare da tana tangal-tangal da su ba.

فَلَمَّا رَأَوْهُ زُلْفَةً سِيٓـَٔتْ وُجُوهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَقِيلَ هَٰذَا ٱلَّذِى كُنتُم
بِهِۦ تَدَّعُونَ ﴿٢٧﴾ قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِنْ أَهْلَكَنِىَ ٱللَّهُ وَمَن مَّعِىَ أَوْ رَحِمَنَا
فَمَن يُجِيرُ ٱلْكَٰفِرِينَ مِنْ عَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿٢٨﴾ قُلْ هُوَ ٱلرَّحْمَٰنُ
ءَامَنَّا بِهِۦ وَعَلَيْهِ تَوَكَّلْنَا ۖ فَسَتَعْلَمُونَ مَنْ هُوَ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ
﴿٢٩﴾ قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِنْ أَصْبَحَ مَآؤُكُمْ غَوْرًا فَمَن يَأْتِيكُم بِمَآءٍ مَّعِينٍ ﴿٣٠﴾

سُورَةُ القَلَمِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

نٓ ۚ وَٱلْقَلَمِ وَمَا يَسْطُرُونَ ﴿١﴾ مَآ أَنتَ بِنِعْمَةِ رَبِّكَ بِمَجْنُونٍ ﴿٢﴾ وَإِنَّ
لَكَ لَأَجْرًا غَيْرَ مَمْنُونٍ ﴿٣﴾ وَإِنَّكَ لَعَلَىٰ خُلُقٍ عَظِيمٍ ﴿٤﴾ فَسَتُبْصِرُ
وَيُبْصِرُونَ ﴿٥﴾ بِأَيِّيكُمُ ٱلْمَفْتُونُ ﴿٦﴾ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعْلَمُ بِمَن ضَلَّ
عَن سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعْلَمُ بِٱلْمُهْتَدِينَ ﴿٧﴾ فَلَا تُطِعِ ٱلْمُكَذِّبِينَ
﴿٨﴾ وَدُّوا۟ لَوْ تُدْهِنُ فَيُدْهِنُونَ ﴿٩﴾ وَلَا تُطِعْ كُلَّ حَلَّافٍ مَّهِينٍ
﴿١٠﴾ هَمَّازٍ مَّشَّآءٍۭ بِنَمِيمٍ ﴿١١﴾ مَّنَّاعٍ لِّلْخَيْرِ مُعْتَدٍ أَثِيمٍ ﴿١٢﴾
عُتُلٍّۭ بَعْدَ ذَٰلِكَ زَنِيمٍ ﴿١٣﴾ أَن كَانَ ذَا مَالٍ وَبَنِينَ ﴿١٤﴾ إِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِ
ءَايَٰتُنَا قَالَ أَسَٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿١٥﴾ سَنَسِمُهُۥ عَلَى ٱلْخُرْطُومِ ﴿١٦﴾

(27) To lokacin da za su gan shi a kurkusa, sai fuskokin waɗanda suka kafirce suka yi baƙi, aka kuma ce: “Wannan ne abin da kuka kasance kuna neman zuwansa.”
(28) Ka ce: “Ku ba ni labari, idan Allah Ya hallaka ni da waɗanda suke tare da ni, ko kuma Ya ji ƙan mu, to wane ne zai kare kafirai daga azaba mai raɗaɗi?”
(29) Ka ce: “Shi ne (Allah) Mai rahama, mun yi imani da Shi, kuma a gare Shi muka dogara, to da sannu za ku san shin wane ne yake cikin ɓata mabayyani?”
(30) Ka ce: “Ku ba ni labari, idan ruwanku ya wayi gari a ƙafe, to wane ne zai zo muku da ruwa mai ɓuɓɓugowa?”

Sura Kalam

(1) NUN[1]. (Allah ya ce): Na rantse da alƙalami da abin da (mala’iku) suke rubutawa
(2) Kai ba mahaukaci ba ne saboda ni’imar Ubangijinka
(3) Kuma lalle tabbas kana da lada marar yankewa
(4) Lalle kuma kai kana kan halaye masu girma
(5) To ba da daɗewa ba za ka gani, su ma kuma su gani
(6) Wane ne daga cikinku mahaukaci?
(7) Lalle Ubangijinka Shi Ya fi sanin wanda ya kauce wa hanyarsa kuma Shi Ya fi sanin shiryayyu
(8) Saboda haka kada ka bi masu ƙaryatawa
(9) Sun yi burin da za ka sassauto, sai su ma su sassauto[2]
(10) Kada kuma ka bi duk wani mai yawan rantsuwa, wulaƙantacce
(11) Mai yawan yin zunɗe, mai yawan yawo da annamimanci
(12) Mai yawan hana alheri, mai ta’addanci, mai yawan saɓo
(13) Mai busasshiyar zuciya, bayan wannan kuma marar asali ne
(14) Don ya kasance mai dukiya da ‘ya’ya
(15) Idan ana karanta masa ayoyinmu sai ya ce: “Tatsuniyoyin mutanen farko ne.”
(16) Ba da daɗewa ba za Mu yi masa alama a kan hancinsa

(1) Duba Suratul Baƙara, aya ta 1, hashiya ta 8.

(2) Watau ya daina aibata gumakansu da bautarsu, sai su ma su daina sukan sa da addininsa.

إِنَّا بَلَوْنَٰهُمْ كَمَا بَلَوْنَآ أَصْحَٰبَ ٱلْجَنَّةِ إِذْ أَقْسَمُوا۟ لَيَصْرِمُنَّهَا مُصْبِحِينَ ﴿١٧﴾ وَلَا
يَسْتَثْنُونَ ﴿١٨﴾ فَطَافَ عَلَيْهَا طَآئِفٌ مِّن رَّبِّكَ وَهُمْ نَآئِمُونَ ﴿١٩﴾ فَأَصْبَحَتْ
كَٱلصَّرِيمِ ﴿٢٠﴾ فَتَنَادَوْا۟ مُصْبِحِينَ ﴿٢١﴾ أَنِ ٱغْدُوا۟ عَلَىٰ حَرْثِكُمْ إِن كُنتُمْ
صَٰرِمِينَ ﴿٢٢﴾ فَٱنطَلَقُوا۟ وَهُمْ يَتَخَٰفَتُونَ ﴿٢٣﴾ أَن لَّا يَدْخُلَنَّهَا ٱلْيَوْمَ عَلَيْكُم
مِّسْكِينٌ ﴿٢٤﴾ وَغَدَوْا۟ عَلَىٰ حَرْدٍ قَٰدِرِينَ ﴿٢٥﴾ فَلَمَّا رَأَوْهَا قَالُوٓا۟ إِنَّا لَضَآلُّونَ
﴿٢٦﴾ بَلْ نَحْنُ مَحْرُومُونَ ﴿٢٧﴾ قَالَ أَوْسَطُهُمْ أَلَمْ أَقُل لَّكُمْ لَوْلَا تُسَبِّحُونَ
﴿٢٨﴾ قَالُوا۟ سُبْحَٰنَ رَبِّنَآ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ﴿٢٩﴾ فَأَقْبَلَ بَعْضُهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ
يَتَلَٰوَمُونَ ﴿٣٠﴾ قَالُوا۟ يَٰوَيْلَنَآ إِنَّا كُنَّا طَٰغِينَ ﴿٣١﴾ عَسَىٰ رَبُّنَآ أَن يُبْدِلَنَا
خَيْرًا مِّنْهَآ إِنَّآ إِلَىٰ رَبِّنَا رَٰغِبُونَ ﴿٣٢﴾ كَذَٰلِكَ ٱلْعَذَابُ ۖ وَلَعَذَابُ ٱلْءَاخِرَةِ
أَكْبَرُ ۘ لَوْ كَانُوا۟ يَعْلَمُونَ ﴿٣٣﴾ إِنَّ لِلْمُتَّقِينَ عِندَ رَبِّهِمْ جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ﴿٣٤﴾
أَفَنَجْعَلُ ٱلْمُسْلِمِينَ كَٱلْمُجْرِمِينَ ﴿٣٥﴾ مَا لَكُمْ كَيْفَ تَحْكُمُونَ ﴿٣٦﴾ أَمْ لَكُمْ
كِتَٰبٌ فِيهِ تَدْرُسُونَ ﴿٣٧﴾ إِنَّ لَكُمْ فِيهِ لَمَا تَخَيَّرُونَ ﴿٣٨﴾ أَمْ لَكُمْ أَيْمَٰنٌ عَلَيْنَا
بَٰلِغَةٌ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ ۙ إِنَّ لَكُمْ لَمَا تَحْكُمُونَ ﴿٣٩﴾ سَلْهُمْ أَيُّهُم بِذَٰلِكَ
زَعِيمٌ ﴿٤٠﴾ أَمْ لَهُمْ شُرَكَآءُ فَلْيَأْتُوا۟ بِشُرَكَآئِهِمْ إِن كَانُوا۟ صَٰدِقِينَ ﴿٤١﴾ يَوْمَ
يُكْشَفُ عَن سَاقٍ وَيُدْعَوْنَ إِلَى ٱلسُّجُودِ فَلَا يَسْتَطِيعُونَ ﴿٤٢﴾

(17) Lalle Mu Mun jarrabe su (wato mutanen Makka) kamar yadda Muka jarrabi ma'abota gona, lokacin da suka rantse cewa, lalle tabbas za su girbe ta da asussuba
(18) Ba sa kuma togaciya (da fadar insha Allah)
(19) Sai wani bala'i daga Ubangijinka ya kewaye ta alhali su suna bacci
(20) Sai ta wayi gari (baki kirin) kamar duhun dare
(21) Sai suka kirawo junansu da asussuba
(22) Cewa: "Ku yi sammako ga amfanin gonarku idan kun kasance masu yin girbi."
(23)Sai suka tafi alhali suna yi wa junansu rada (24) Cewa: "Lalle a yau kada wani miskini ya shigar muku cikinta." (25) Suka kuwa yi sammako suna masu zaton su masu iko ne a kan hana (mabukata) (26) To lokacin da suka gan ta sai suka ce: "Lalle mu tabbas mun yi batan kai (27) "A'a, mu dai an hana mu ne kawai." (28) Sai wanda ya fi su kirki ya ce: "Ban gaya muku ya kamata ku tsarkake Allah ba?" (29) Suka ce, "Tsarki ya tabbata ga Ubangijinmu, lalle mu mun kasance azzalumai." (30) Sai sashinsu ya fuskanci sashi suna zargin juna (31) Suka ce: "Kaiconmu, lalle mu mun kasance masu shisshigi (32) "Tsammanin Ubangijinmu zai musanya mana wadda ta fi ta, lalle mu masu kwadayi ne a wurin Ubangijinmu[1]." (33) Kamar haka ne azaba take tabbata; kuma tabbas azabar lahira ta fi girma. Da sun kasance sun san haka (34) Lalle masu takawa suna da gidajen Aljannar ni'ima a wurin Ubangijinsu (35) Yanzu za Mu sanya Musulmi kamar kangararru? (36) Me ya same ku ne, yaya kuke irin wannan hukuncin?
(37) Ko kuna da wani littafi ne wanda a cikinsa kuke karantawa?
(38) (Cewa) a cikinsa lalle kuna da abin da kuke zaba? (39) Ko kuwa kuna da wasu alkawura na rantsuwa ne (tabbatattu) a kanmu har zuwa ranar alkiyama cewa, lalle kuna da abin da kuke hukunta wa (kanku)?
(40) Ka tambaye su wane ne a cikinsu ya yi lamuni game da wannan?
(41) Ko kuwa suna da wasu ababan tarayya ne? To su kawo ababan tarayyar tasu idan sun kasance masu gaskiya (42) (Ka tuna) ranar da za a yaye kwauri[2] a kuma kirawo su zuwa yin sujjada sannan su rasa ikon yi

(1) Watau zai ba su wata gonar da ta fi tasu, suna kuma fatan zai yi musu afuwa ya yafe musu kurakuransu.

(2) Watau ranar da Allah ( ) zai kware kwaurinsa mai daraja wanda bai yi kama da wani abu na halittarsa ba.



خَٰشِعَةً أَبۡصَٰرُهُمۡ تَرۡهَقُهُمۡ ذِلَّةٞۖ وَقَدۡ كَانُواْ يُدۡعَوۡنَ إِلَى ٱلسُّجُودِ وَهُمۡ
سَٰلِمُونَ ﴿٤٣﴾ فَذَرۡنِي وَمَن يُكَذِّبُ بِهَٰذَا ٱلۡحَدِيثِۖ سَنَسۡتَدۡرِجُهُم
مِّنۡ حَيۡثُ لَا يَعۡلَمُونَ ﴿٤٤﴾ وَأُمۡلِي لَهُمۡۚ إِنَّ كَيۡدِي مَتِينٌ ﴿٤٥﴾ أَمۡ تَسۡـَٔلُهُمۡ
أَجۡرٗا فَهُم مِّن مَّغۡرَمٖ مُّثۡقَلُونَ ﴿٤٦﴾ أَمۡ عِندَهُمُ ٱلۡغَيۡبُ فَهُمۡ يَكۡتُبُونَ
﴿٤٧﴾ فَٱصۡبِرۡ لِحُكۡمِ رَبِّكَ وَلَا تَكُن كَصَاحِبِ ٱلۡحُوتِ إِذۡ نَادَىٰ
وَهُوَ مَكۡظُومٞ ﴿٤٨﴾ لَّوۡلَآ أَن تَدَٰرَكَهُۥ نِعۡمَةٞ مِّن رَّبِّهِۦ لَنُبِذَ بِٱلۡعَرَآءِ
وَهُوَ مَذۡمُومٞ ﴿٤٩﴾ فَٱجۡتَبَٰهُ رَبُّهُۥ فَجَعَلَهُۥ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ
﴿٥٠﴾ وَإِن يَكَادُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَيُزۡلِقُونَكَ بِأَبۡصَٰرِهِمۡ لَمَّا سَمِعُواْ
ٱلذِّكۡرَ وَيَقُولُونَ إِنَّهُۥ لَمَجۡنُونٞ ﴿٥١﴾ وَمَا هُوَ إِلَّا ذِكۡرٞ لِّلۡعَٰلَمِينَ ﴿٥٢﴾

سُورَةُ الحَاقَّةِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلۡحَآقَّةُ ﴿١﴾ مَا ٱلۡحَآقَّةُ ﴿٢﴾ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡحَآقَّةُ ﴿٣﴾ كَذَّبَتۡ ثَمُودُ وَعَادُۢ
بِٱلۡقَارِعَةِ ﴿٤﴾ فَأَمَّا ثَمُودُ فَأُهۡلِكُواْ بِٱلطَّاغِيَةِ ﴿٥﴾ وَأَمَّا عَادٞ فَأُهۡلِكُواْ بِرِيحٖ
صَرۡصَرٍ عَاتِيَةٖ ﴿٦﴾ سَخَّرَهَا عَلَيۡهِمۡ سَبۡعَ لَيَالٖ وَثَمَٰنِيَةَ أَيَّامٍ حُسُومٗاۖ فَتَرَى
ٱلۡقَوۡمَ فِيهَا صَرۡعَىٰ كَأَنَّهُمۡ أَعۡجَازُ نَخۡلٍ خَاوِيَةٖ ﴿٧﴾ فَهَلۡ تَرَىٰ لَهُم مِّنۢ بَاقِيَةٖ ﴿٨﴾

(43) Idanuwansu a ƙaskance, wulaƙanci ya lulluɓe su. Haƙiƙa kuwa a duniya sun kasance ana kiran su zuwa yin sujjada alhali suna lafiyayyu
(44) Saboda haka ka bar Ni da wanda yake ƙaryata wannan Alƙur'ani; ba da daɗewa ba za Mu yi musu talala ta inda ba za su sani ba
(45) Kuma zan saurara musu. Lalle kaidina mai ƙarfi ne
(46) Ko kuwa kana tambayar su wani lada ne, saboda haka biyan (wannan lada) ya yi musu nauyi?
(47) Ko kuwa sanin gaibu a wurinsu yake, saboda haka suke rubuto shi?
(48) To ka yi haƙuri da hukuncin Ubangijinka, kada ka zama kamar ma'abocin kifi (Yunus) a yayin da ya yi kira, alhali shi yana cike da baƙin ciki
(49) Ba don wata rahama daga Ubangijinsa ta riske shi ba, da an jefar da shi a ƙungurmin daji alhali shi yana abin suka
(50) Sai Ubangijinsa Ya zaɓe shi Ya sanya shi daga (bayi) nagari
(51) Lalle kuma waɗanda suka kafirta sun yi kusa su kayar da kai da kallonsu yayin da suka ji Alƙur'ani, suka kuma riƙa cewa: "Lalle shi tabbas mahaukaci ne!"
(52) Shi kuwa (Alƙur'ani) ba wani abu ba ne face gargaɗi ga talikai

---

Sura Haƙƙa

(1) Mai tabbata (watau alƙiyama)
(2) Mece ce mai tabbata?
(3) Me ya sanar da kai abin da ake kira mai tabbata?
(4) Samudawa da Adawa sun ƙaryata mai ƙwanƙwasa (zukata da tsoro)
(5) To amma Samudawa sai aka halaka su da tsawa mai tsanani
(6) Adawa kuma sai aka hallaka su da iska mai tsananin sanyi mai ƙarfi
(7) Ya aiko musu da ita dare bakwai da wuni takwas a jere, sai ka riƙa ganin mutane a cikinta matattu a yashe, kai ka ce rarakakkun kututturan dabinai ne (a zube)
(8) To shin za ka iya ganin sauran ɓurɓushinsu?

وَجَآءَ فِرْعَوْنُ وَمَن قَبْلَهُۥ وَٱلْمُؤْتَفِكَٰتُ بِٱلْخَاطِئَةِ ﴿٩﴾ فَعَصَوْا۟ رَسُولَ
رَبِّهِمْ فَأَخَذَهُمْ أَخْذَةً رَّابِيَةً ﴿١٠﴾ إِنَّا لَمَّا طَغَا ٱلْمَآءُ حَمَلْنَٰكُمْ فِى ٱلْجَارِيَةِ
﴿١١﴾ لِنَجْعَلَهَا لَكُمْ تَذْكِرَةً وَتَعِيَهَآ أُذُنٌ وَٰعِيَةٌ ﴿١٢﴾ فَإِذَا نُفِخَ فِى ٱلصُّورِ
نَفْخَةٌ وَٰحِدَةٌ ﴿١٣﴾ وَحُمِلَتِ ٱلْأَرْضُ وَٱلْجِبَالُ فَدُكَّتَا دَكَّةً وَٰحِدَةً ﴿١٤﴾
فَيَوْمَئِذٍ وَقَعَتِ ٱلْوَاقِعَةُ ﴿١٥﴾ وَٱنشَقَّتِ ٱلسَّمَآءُ فَهِىَ يَوْمَئِذٍ وَاهِيَةٌ
﴿١٦﴾ وَٱلْمَلَكُ عَلَىٰٓ أَرْجَآئِهَا ۚ وَيَحْمِلُ عَرْشَ رَبِّكَ فَوْقَهُمْ يَوْمَئِذٍ ثَمَٰنِيَةٌ
﴿١٧﴾ يَوْمَئِذٍ تُعْرَضُونَ لَا تَخْفَىٰ مِنكُمْ خَافِيَةٌ ﴿١٨﴾ فَأَمَّا مَنْ أُوتِىَ كِتَٰبَهُۥ
بِيَمِينِهِۦ فَيَقُولُ هَآؤُمُ ٱقْرَءُوا۟ كِتَٰبِيَهْ ﴿١٩﴾ إِنِّى ظَنَنتُ أَنِّى مُلَٰقٍ حِسَابِيَهْ
﴿٢٠﴾ فَهُوَ فِى عِيشَةٍ رَّاضِيَةٍ ﴿٢١﴾ فِى جَنَّةٍ عَالِيَةٍ ﴿٢٢﴾ قُطُوفُهَا دَانِيَةٌ ﴿٢٣﴾
كُلُوا۟ وَٱشْرَبُوا۟ هَنِيٓـًٔۢا بِمَآ أَسْلَفْتُمْ فِى ٱلْأَيَّامِ ٱلْخَالِيَةِ ﴿٢٤﴾ وَأَمَّا مَنْ أُوتِىَ
كِتَٰبَهُۥ بِشِمَالِهِۦ فَيَقُولُ يَٰلَيْتَنِى لَمْ أُوتَ كِتَٰبِيَهْ ﴿٢٥﴾ وَلَمْ أَدْرِ مَا حِسَابِيَهْ
﴿٢٦﴾ يَٰلَيْتَهَا كَانَتِ ٱلْقَاضِيَةَ ﴿٢٧﴾ مَآ أَغْنَىٰ عَنِّى مَالِيَهْ ﴿٢٨﴾ هَلَكَ عَنِّى سُلْطَٰنِيَهْ
﴿٢٩﴾ خُذُوهُ فَغُلُّوهُ ﴿٣٠﴾ ثُمَّ ٱلْجَحِيمَ صَلُّوهُ ﴿٣١﴾ ثُمَّ فِى سِلْسِلَةٍ ذَرْعُهَا
سَبْعُونَ ذِرَاعًا فَٱسْلُكُوهُ ﴿٣٢﴾ إِنَّهُۥ كَانَ لَا يُؤْمِنُ بِٱللَّهِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٣٣﴾
وَلَا يَحُضُّ عَلَىٰ طَعَامِ ٱلْمِسْكِينِ ﴿٣٤﴾ فَلَيْسَ لَهُ ٱلْيَوْمَ هَٰهُنَا حَمِيمٌ ﴿٣٥﴾

(9) Fir’auna kuma da waɗanda suke gabaninsa da (alƙaryar) da aka kifar(1), sun zo da manyan laifuka
(10) Sai suka saɓa wa Manzon Ubangijinsu, sai Muka kama su kamawa mai ƙaruwa
(11) Mu lalle yayin da ruwa ya mamaye komai Mun ɗauke ku a cikin jirgin ruwa(2)
(12) Don Mu sanya shi wa’azi a gare ku, kuma kunne mai kiyayewa ya kiyaye shi
(13) To idan aka busa ƙaho busa ɗaya
(14) Aka kuma ɗaga ƙasa da duwatsu sai aka dandaƙe su dandaƙewa baki ɗaya
(15) To a wannan rana ce mai afkuwa ta afku (watau alƙiyama)
(16) Sama kuma ta kekkece, don kuwa a wannan ranar ita mai rauni ce
(17) Mala’iku kuma suna a sasanninta. A wannan ranar kuma (mala’iku) takwas za su ɗauki Al’arshin Ubangijinka a samansu
(18) A wannan ranar ne kuma za a bujuro da ku, ba wani abu naku mai ɓuya
(19) To duk wanda aka bai wa littafinsa a hannunsa na dama zai ce: “Ku karɓi littafina ku karanta
(20) “Lalle ni na tabbata haka zan haɗu da sakamakona.”
(21) To shi zai zama cikin rayuwa abar yarda
(22) Cikin Aljanna maɗaukakiya
(23) ‘Ya’yan itatuwanta dab da dab suke
(24) (A ce da su): “Ku ci ku sha kuna masu farin ciki saboda abin da kuka gabatar a kwanakinku da suka shuɗe (na duniya).”
(25) Amma kuma wanda aka bai wa littafinsa a hannunsa na hagun sai ya ce: “Kaicona, ina ma da ba a ba ni littafina ba!
(26) “Kuma ban san mene ne sakamakona ba
(27) “Kaiconta (watau mutuwa), ina ma da ta zama ita ce ƙarshe!
(28) “Dukiyata ba ta wadata min komai ba
(29) “Mulkina ya ɓace min da gani.”
(30) (Sai a ce da mala’iku): Ku kama shi ku ƙuƙunce shi!
(31) Sannan ku shigar da shi (wutar) Jahimu
(32) Sannan ku sa shi cikin sarƙa mai tsawo kamu saba’in
(33) Lalle shi ya kasance ba ya imani da Allah Mai girma
(34) Ba ya kuma kwaɗaitarwa bisa ciyar da mabuƙaci
(35) To a yau ba shi da wani masoyi a nan

(1) Watau alƙaryun Annabi Luɗ ( ) waɗanda Allah ( ) ya kifar da su saboda miyagun laifuffukansu.

(2) Watau ya ɗauki iyayensu waɗanda suke cikin tsatsonsu a cikin jirgin ruwan Annabi Nuhu ( ).


وَلَا طَعَامٌ إِلَّا مِنْ غِسْلِينٍ ﴿٣٦﴾ لَّا يَأْكُلُهُۥٓ إِلَّا ٱلْخَٰطِـُٔونَ ﴿٣٧﴾ فَلَآ أُقْسِمُ
بِمَا تُبْصِرُونَ ﴿٣٨﴾ وَمَا لَا تُبْصِرُونَ ﴿٣٩﴾ إِنَّهُۥ لَقَوْلُ رَسُولٍ كَرِيمٍ ﴿٤٠﴾ وَمَا هُوَ
بِقَوْلِ شَاعِرٍ ۚ قَلِيلًا مَّا تُؤْمِنُونَ ﴿٤١﴾ وَلَا بِقَوْلِ كَاهِنٍ ۚ قَلِيلًا مَّا تَذَكَّرُونَ
﴿٤٢﴾ تَنزِيلٌ مِّن رَّبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٤٣﴾ وَلَوْ تَقَوَّلَ عَلَيْنَا بَعْضَ ٱلْأَقَاوِيلِ ﴿٤٤﴾
لَأَخَذْنَا مِنْهُ بِٱلْيَمِينِ ﴿٤٥﴾ ثُمَّ لَقَطَعْنَا مِنْهُ ٱلْوَتِينَ ﴿٤٦﴾ فَمَا مِنكُم
مِّنْ أَحَدٍ عَنْهُ حَٰجِزِينَ ﴿٤٧﴾ وَإِنَّهُۥ لَتَذْكِرَةٌ لِّلْمُتَّقِينَ ﴿٤٨﴾ وَإِنَّا
لَنَعْلَمُ أَنَّ مِنكُم مُّكَذِّبِينَ ﴿٤٩﴾ وَإِنَّهُۥ لَحَسْرَةٌ عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ
﴿٥٠﴾ وَإِنَّهُۥ لَحَقُّ ٱلْيَقِينِ ﴿٥١﴾ فَسَبِّحْ بِٱسْمِ رَبِّكَ ٱلْعَظِيمِ ﴿٥٢﴾

سُورَةُ المَعَارِجِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

سَأَلَ سَآئِلٌۢ بِعَذَابٍ وَاقِعٍ ﴿١﴾ لِّلْكَٰفِرِينَ لَيْسَ لَهُۥ دَافِعٌ ﴿٢﴾
مِّنَ ٱللَّهِ ذِى ٱلْمَعَارِجِ ﴿٣﴾ تَعْرُجُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَٱلرُّوحُ إِلَيْهِ
فِى يَوْمٍ كَانَ مِقْدَارُهُۥ خَمْسِينَ أَلْفَ سَنَةٍ ﴿٤﴾ فَٱصْبِرْ صَبْرًا جَمِيلًا
﴿٥﴾ إِنَّهُمْ يَرَوْنَهُۥ بَعِيدًا ﴿٦﴾ وَنَرَىٰهُ قَرِيبًا ﴿٧﴾ يَوْمَ تَكُونُ ٱلسَّمَآءُ
كَٱلْمُهْلِ ﴿٨﴾ وَتَكُونُ ٱلْجِبَالُ كَٱلْعِهْنِ ﴿٩﴾ وَلَا يَسْـَٔلُ حَمِيمٌ حَمِيمًا ﴿١٠﴾

(36) Kuma ba shi da wani abinci sai na mugunyar ‘yan wuta
(37) Ba mai cin ta sai masu laifukan ganganci
(38) Ina yin rantsuwa da abin da kuke gani
(39) Da kuma abin da ba kwa gani
(40) Lalle shi (Alƙur’ani) tabbas zance ne na wani manzo mai girma
(41) Shi kuwa ba zancen mawaƙi ba ne. Kaɗan ne ƙwarai kuke yin imani
(42) Ba kuma zance ne na boka ba. Kaɗan ne ƙwarai kuke wa’azantuwa
(43) Shi saukakke ne daga Ubangijin halittu
(44) Kuma da ya ƙaga Mana wasu maganganu
(45) Tabbas da Mun kama shi da ƙarfi
(46) Sannan da Mun yanke masa jijiyar zuciyarsa
(47) Sannan kuma ba wani ɗaya daga cikinku da zai kare shi
(48) Lalle shi (Alƙur’ani) wa’azi ne ga masu kiyaye dokokin Allah
(49) Lalle kuma Mu Muna sane da cewa a cikinku akwai masu ƙaryatawa
(50) Kuma lalle shi tabbas nadama ce ga kafirai
(51) Kuma lalle shi tabbas gaskiya ce ta sakankancewa
(52) Saboda haka ka yi tasbihi da sunan Ubangijinka Mai girma

Sura Ma’arij

(1) Mai tambaya ya yi tambaya game da wata azaba mai aukuwa(1)
(2) Ga kafirai (wadda) ba ta da wani mai kaɗe ta
(3) Daga Allah Mai matattakalai
(4) Mala’iku tare da Jibrilu suna hawa zuwa gare Shi a cikin wata rana (wadda) gwargwadonta yake daidai da shekara dubu hamsin
(5) Sai ka yi haƙuri kyakkyawan haƙuri
(6) Lalle su suna ganin ta mai nisa ce
(7) Mu kuma Muna ganin ta kusa-kusa
(8) A ranar da sama za ta kasance kamar narkakkiyar dalma
(9) Duwatsu kuma su zama kamar kaɗaɗɗiyar auduga (ta gashin tumaki)
(10) Kuma aboki ba ya tambayar aboki

(1) Watau wadda Annabi ( ) yake musu kashedi da ita idan sun ƙi imani. Duba Suratul Anfal, aya ta 32. Mai tambayar kuwa shi ne Nadhru ɗan Haris.

يُبَصَّرُونَهُمْ ۚ يَوَدُّ ٱلْمُجْرِمُ لَوْ يَفْتَدِى مِنْ عَذَابِ يَوْمِئِذٍۭ بِبَنِيهِ ﴿١١﴾
وَصَٰحِبَتِهِۦ وَأَخِيهِ ﴿١٢﴾ وَفَصِيلَتِهِ ٱلَّتِى تُـْٔوِيهِ ﴿١٣﴾ وَمَن فِى ٱلْأَرْضِ جَمِيعًا
ثُمَّ يُنجِيهِ ﴿١٤﴾ كَلَّآ ۖ إِنَّهَا لَظَىٰ ﴿١٥﴾ نَزَّاعَةً لِّلشَّوَىٰ ﴿١٦﴾ تَدْعُوا۟ مَنْ أَدْبَرَ
وَتَوَلَّىٰ ﴿١٧﴾ وَجَمَعَ فَأَوْعَىٰٓ ﴿١٨﴾ ۞ إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ خُلِقَ هَلُوعًا ﴿١٩﴾ إِذَا مَسَّهُ ٱلشَّرُّ
جَزُوعًا ﴿٢٠﴾ وَإِذَا مَسَّهُ ٱلْخَيْرُ مَنُوعًا ﴿٢١﴾ إِلَّا ٱلْمُصَلِّينَ ﴿٢٢﴾ ٱلَّذِينَ هُمْ
عَلَىٰ صَلَاتِهِمْ دَآئِمُونَ ﴿٢٣﴾ وَٱلَّذِينَ فِىٓ أَمْوَٰلِهِمْ حَقٌّ مَّعْلُومٌ ﴿٢٤﴾ لِّلسَّآئِلِ
وَٱلْمَحْرُومِ ﴿٢٥﴾ وَٱلَّذِينَ يُصَدِّقُونَ بِيَوْمِ ٱلدِّينِ ﴿٢٦﴾ وَٱلَّذِينَ هُم مِّنْ عَذَابِ
رَبِّهِم مُّشْفِقُونَ ﴿٢٧﴾ إِنَّ عَذَابَ رَبِّهِمْ غَيْرُ مَأْمُونٍ ﴿٢٨﴾ وَٱلَّذِينَ هُمْ
لِفُرُوجِهِمْ حَٰفِظُونَ ﴿٢٩﴾ إِلَّا عَلَىٰٓ أَزْوَٰجِهِمْ أَوْ مَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُهُمْ
فَإِنَّهُمْ غَيْرُ مَلُومِينَ ﴿٣٠﴾ فَمَنِ ٱبْتَغَىٰ وَرَآءَ ذَٰلِكَ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْعَادُونَ ﴿٣١﴾
وَٱلَّذِينَ هُمْ لِأَمَٰنَٰتِهِمْ وَعَهْدِهِمْ رَٰعُونَ ﴿٣٢﴾ وَٱلَّذِينَ هُم بِشَهَٰدَٰتِهِمْ قَآئِمُونَ
﴿٣٣﴾ وَٱلَّذِينَ هُمْ عَلَىٰ صَلَاتِهِمْ يُحَافِظُونَ ﴿٣٤﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ فِى جَنَّٰتٍ مُّكْرَمُونَ ﴿٣٥﴾
فَمَالِ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ قِبَلَكَ مُهْطِعِينَ ﴿٣٦﴾ عَنِ ٱلْيَمِينِ وَعَنِ ٱلشِّمَالِ
عِزِينَ ﴿٣٧﴾ أَيَطْمَعُ كُلُّ ٱمْرِئٍ مِّنْهُمْ أَن يُدْخَلَ جَنَّةَ نَعِيمٍ ﴿٣٨﴾ كَلَّآ ۖ إِنَّا خَلَقْنَٰهُم
مِّمَّا يَعْلَمُونَ ﴿٣٩﴾ فَلَآ أُقْسِمُ بِرَبِّ ٱلْمَشَٰرِقِ وَٱلْمَغَٰرِبِ إِنَّا لَقَٰدِرُونَ ﴿٤٠﴾

(11) (Alhali kuma) ana nuna musu junansu. Mai laifi ya rika burin ina ma zai fanshi kansa daga azabar wannan rana da 'ya'yansa
(12) Da matarsa da ɗan'uwansa
(13) Da danginsa waɗanda suke kare shi
(14) Da ma duk wanda yake a bayan ƙasa baki ɗaya, sannan (fansar) ta tserar da shi
(15) Faufau! Lalle ita (wutar) Laza ce
(16) Mai ɗaddaye fatar kai
(17) Tana kiran wanda ya juya ya ba da baya
(18) Ya kuma tara (dukiya) sai ya ɓoye (ta)
(19) Lalle mutum an halicce shi mai rashin nutsuwa ne
(20) (Watau) idan sharri ya same shi ya zama mai raki
(21) Idan kuma alheri ya same shi ya zama mai maƙo
(22) Sai dai masallata
(23) Waɗanda suke masu dawwama a kan sallarsu
(24) Waɗanda kuma suke akwai haƙƙi sananne a cikin dukiyoyinsu
(25) Ga mai roƙo da wanda ake hana wa (saboda ba ya roƙo)
(26) Waɗanda kuma suke gaskata ranar sakamako
(27) Waɗanda kuma suke tsoron azabar Ubangijinsu
(28) Lalle azabar Ubangijinsu ba abar amincewa ba ce
(29) Waɗanda kuma suke kiyaye al'aurarsu (daga yin zina)
(30) Sai a wajan matayensu ko kuma ƙwarƙarorinsu; to su a nan ba ababen zargi ba ne
(31) To duk wanda ya nemi (wani abu) bayan wannan, to waɗannan su ne masu ƙetare iyaka
(32) Waɗanda kuma suke kiyaye amanoninsu da alƙawuransu
(33) Waɗanda kuma suke tsai da shaidarsu
(34) Waɗanda kuma suke kiyaye sallolinsu
(35) Waɗannan su ne waɗanda ake girmamawa cikin gidajen Aljanna
(36) To me ya sami waɗanda suka kafirta suke gaggawa zuwa gare ka?
(37) Kungiya-ƙungiya, ta damanka da ta hagunka
(38) Yanzu ashe kowane mutum daga cikinsu yana kwaɗayin a shigar da shi Aljannar ni'ima?
(39) Faufau! Lalle Mu Mun halitta su daga abin da suka sani.(1)
(40) To, ina yin rantsuwa da Ubangijin wuraren hudowar rana da wuraren faɗuwarta, lalle Mu Masu iko ne

(1) Watau wulaƙantaccen ruwa na maniyyi.

عَلَىٰٓ أَن نُّبَدِّلَ خَيْرًا مِّنْهُمْ وَمَا نَحْنُ بِمَسْبُوقِينَ ﴿٤١﴾ فَذَرْهُمْ
يَخُوضُوا۟ وَيَلْعَبُوا۟ حَتَّىٰ يُلَٰقُوا۟ يَوْمَهُمُ ٱلَّذِى يُوعَدُونَ ﴿٤٢﴾ يَوْمَ
يَخْرُجُونَ مِنَ ٱلْأَجْدَاثِ سِرَاعًا كَأَنَّهُمْ إِلَىٰ نُصُبٍ يُوفِضُونَ ﴿٤٣﴾
خَٰشِعَةً أَبْصَٰرُهُمْ تَرْهَقُهُمْ ذِلَّةٌ ۚ ذَٰلِكَ ٱلْيَوْمُ ٱلَّذِى كَانُوا۟ يُوعَدُونَ ﴿٤٤﴾

سُورَةُ نُوحٍ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِنَّآ أَرْسَلْنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوْمِهِۦٓ أَنْ أَنذِرْ قَوْمَكَ مِن قَبْلِ أَن يَأْتِيَهُمْ
عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿١﴾ قَالَ يَٰقَوْمِ إِنِّى لَكُمْ نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿٢﴾ أَنِ ٱعْبُدُوا۟
ٱللَّهَ وَٱتَّقُوهُ وَأَطِيعُونِ ﴿٣﴾ يَغْفِرْ لَكُم مِّن ذُنُوبِكُمْ وَيُؤَخِّرْكُمْ
إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى ۚ إِنَّ أَجَلَ ٱللَّهِ إِذَا جَآءَ لَا يُؤَخَّرُ ۖ لَوْ كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٤﴾
قَالَ رَبِّ إِنِّى دَعَوْتُ قَوْمِى لَيْلًا وَنَهَارًا ﴿٥﴾ فَلَمْ يَزِدْهُمْ دُعَآءِىٓ إِلَّا
فِرَارًا ﴿٦﴾ وَإِنِّى كُلَّمَا دَعَوْتُهُمْ لِتَغْفِرَ لَهُمْ جَعَلُوٓا۟ أَصَٰبِعَهُمْ فِىٓ
ءَاذَانِهِمْ وَٱسْتَغْشَوْا۟ ثِيَابَهُمْ وَأَصَرُّوا۟ وَٱسْتَكْبَرُوا۟ ٱسْتِكْبَارًا
﴿٧﴾ ثُمَّ إِنِّى دَعَوْتُهُمْ جِهَارًا ﴿٨﴾ ثُمَّ إِنِّىٓ أَعْلَنتُ لَهُمْ وَأَسْرَرْتُ
لَهُمْ إِسْرَارًا ﴿٩﴾ فَقُلْتُ ٱسْتَغْفِرُوا۟ رَبَّكُمْ إِنَّهُۥ كَانَ غَفَّارًا ﴿١٠﴾

(41) A kan Mu musanya wasu fiye da su, kuma Mu ba Masu kasawa ba ne
(42) To ka ƙyale su su kutsa su yi wasa har sai sun haɗu da ranarsu wadda ake yi musu alƙawarinta
(43) A ranar da za su fito daga ƙaburbura a gurguje, kai ka ce su suna gaggawa ne zuwa ga wata tuta (ta matattara)
(44) Idanuwansu a ƙasƙance, wulaƙanci ya lulluɓe su. Wannan ne ranar da ake yi musu alƙawarinta

Sura Nuh

(1) Lalle Mu Mun aika Nuhu zuwa ga mutanensa cewa: "Ka gargaɗi mutanenka tun kafin azaba mai raɗaɗi ta zo musu."
(2) Ya ce: "Ya ku mutanena, lalle ni mai gargaɗi ne mabayyani a gare ku
(3) "Kan ku bauta wa Allah, ku kiyaye dokokinsa, kuma ku bi ni
(4) "Zai gafarta muku zunubanku, Ya kuma jinkirta muku har zuwa wani lokaci iyakantacce. Lalle ajalin Allah idan ya zo ba a saurarawa; da kun kasance kun san (haka)
(5) Ya ce: "Ya Ubangijina, lalle ni na kira mutanena dare da rana
(6) "To kiran nawa ba abin da ya ƙara musu sai tawaye
(7) "Lalle ni kuma duk sanda na kira su don Ka gafarta musu, sai su sanya 'yan yatsunsu a cikin kunnuwansu, su kuma lulluɓu da tufafinsu(1) kuma su kafe (a kan haka), su yi girman kai matuƙar girman kai
(8) "Sannan lalle na yi kiran su da babbar murya
(9) "Sannan lalle na yi musu a bayyane, na kuma yi musu a ɓoye sosai
(10) "Sai na ce: "Ku nemi gafarar Ubangijinku, lalle Shi Ya kasance Mai yawan gafara ne

(1) Watau don kada su saurari abin da yake faɗa musu, kada kuma su gan shi da idanuwansu.

يُرْسِلِ ٱلسَّمَآءَ عَلَيْكُم مِّدْرَارًا ﴿١١﴾ وَيُمْدِدْكُم بِأَمْوَٰلٍ وَبَنِينَ وَيَجْعَل
لَّكُمْ جَنَّٰتٍ وَيَجْعَل لَّكُمْ أَنْهَٰرًا ﴿١٢﴾ مَّا لَكُمْ لَا تَرْجُونَ لِلَّهِ وَقَارًا ﴿١٣﴾
وَقَدْ خَلَقَكُمْ أَطْوَارًا ﴿١٤﴾ أَلَمْ تَرَوْا۟ كَيْفَ خَلَقَ ٱللَّهُ سَبْعَ سَمَٰوَٰتٍ
طِبَاقًا ﴿١٥﴾ وَجَعَلَ ٱلْقَمَرَ فِيهِنَّ نُورًا وَجَعَلَ ٱلشَّمْسَ سِرَاجًا ﴿١٦﴾
وَٱللَّهُ أَنۢبَتَكُم مِّنَ ٱلْأَرْضِ نَبَاتًا ﴿١٧﴾ ثُمَّ يُعِيدُكُمْ فِيهَا وَيُخْرِجُكُمْ
إِخْرَاجًا ﴿١٨﴾ وَٱللَّهُ جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَرْضَ بِسَاطًا ﴿١٩﴾ لِّتَسْلُكُوا۟ مِنْهَا
سُبُلًا فِجَاجًا ﴿٢٠﴾ قَالَ نُوحٌ رَّبِّ إِنَّهُمْ عَصَوْنِى وَٱتَّبَعُوا۟ مَن لَّمْ يَزِدْهُ
مَالُهُۥ وَوَلَدُهُۥٓ إِلَّا خَسَارًا ﴿٢١﴾ وَمَكَرُوا۟ مَكْرًا كُبَّارًا ﴿٢٢﴾ وَقَالُوا۟
لَا تَذَرُنَّ ءَالِهَتَكُمْ وَلَا تَذَرُنَّ وَدًّا وَلَا سُوَاعًا وَلَا يَغُوثَ وَيَعُوقَ
وَنَسْرًا ﴿٢٣﴾ وَقَدْ أَضَلُّوا۟ كَثِيرًا ۖ وَلَا تَزِدِ ٱلظَّٰلِمِينَ إِلَّا ضَلَٰلًا ﴿٢٤﴾
مِّمَّا خَطِيٓـَٔاتِهِمْ أُغْرِقُوا۟ فَأُدْخِلُوا۟ نَارًا فَلَمْ يَجِدُوا۟ لَهُم مِّن دُونِ
ٱللَّهِ أَنصَارًا ﴿٢٥﴾ وَقَالَ نُوحٌ رَّبِّ لَا تَذَرْ عَلَى ٱلْأَرْضِ مِنَ ٱلْكَٰفِرِينَ
دَيَّارًا ﴿٢٦﴾ إِنَّكَ إِن تَذَرْهُمْ يُضِلُّوا۟ عِبَادَكَ وَلَا يَلِدُوٓا۟ إِلَّا فَاجِرًا
كَفَّارًا ﴿٢٧﴾ رَّبِّ ٱغْفِرْ لِى وَلِوَٰلِدَىَّ وَلِمَن دَخَلَ بَيْتِىَ مُؤْمِنًا
وَلِلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ ۗ وَلَا تَزِدِ ٱلظَّٰلِمِينَ إِلَّا تَبَارًا ﴿٢٨﴾

(11) “Zai saukar muku da ruwan sama mai yawa
(12) “Kuma Ya daɗe ku da dukiyoyi da ‘ya’yaye, Ya kuma sanya muku gonaki Ya kuma gudanar muku da ƙoramu
(13) “Me ya same ku ne ba kwa ganin girman Allah?
(14) “Haƙiƙa kuma Ya halicce ku ta mataki-mataki
(15) “Shin ba kwa ganin yadda Allah Ya halicci sammai bakwai rufi-rufi?
(16) “Ya kuma sanya wata mai haske a cikinsu; rana kuma Ya sanya ta fitila?
(17) “Allah ne kuma Ya tsiro da ku daga ƙasa a tsirowa (ta halitta)[1]
(18) “Sannan Ya mayar da ku cikinta, zai kuma fitar da ku haƙiƙar fitarwa
(19) “Kuma Allah Ya sanya muku ƙasa a shimfiɗe
(20) “Don ku riƙa bin manya-manyan hanyoyi a cikinta.”
(21) Nuhu ya ce, “Ya Ubangijina, lalle su sun saɓa mini, sun kuma bi duk wanda dukiyarsa da ‘ya’yansa ba su ƙara masa komai ba sai asara
(22) “Suka kuma shirya makirci babba
(23) “Suka kuma ce: ‘Kada ku bar abubuwan bautarku, kuma lalle kada ku bar Waddu da Suwa’u da Yagusu da Ya’uƙu da Nasaru[2].’
(24) “Haƙiƙa kuwa sun ɓatar da adadi mai yawa; kar kuma Ka ƙari kafirai da komai sai ɓata.”
(25) Saboda saɓonsu ne aka nutsar da su, sai aka shigar da su wuta, don haka, ba su sami wasu mataimaka ba Allah ba
(26) Nuhu ya ce: “Ya Ubangijina, kada Ka bar wani mutum ɗaya daga kafirai a bayan ƙasa
(27) “Lalle idan har Ka bar su, to za su ɓatar da bayinka, kuma ba za su haifi kowa ba sai fajiri mai tsananin kafirci
(28) “Ya Ubangijina, Ka gafarta min ni da mahaifana da kuma waɗanda suka shiga gidana suna muminai, da kuma (sauran) muminai maza da mata, kada kuma Ka ƙari kafirai da komai sai hallaka.”

(1) Watau ya halicce su daga ƙasa ta hanyar halittar babansu Annabi Adamu ( ), suna kuma cin abin da ƙasar ta tsiro da shi.

(2) Waɗannan duk sunayen wasu mutanen kirki ne waliyyai da mutanen Annabi Nuhu ( ) suka sassaƙa gumaka da sunayensu suna bauta musu.

سُورَةُ الجِنِّ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

قُلْ أُوحِيَ إِلَيَّ أَنَّهُ اسْتَمَعَ نَفَرٌ مِّنَ الْجِنِّ فَقَالُوا إِنَّا سَمِعْنَا قُرْآنًا
عَجَبًا ﴿١﴾ يَهْدِي إِلَى الرُّشْدِ فَآمَنَّا بِهِ ۖ وَلَن نُّشْرِكَ بِرَبِّنَا أَحَدًا ﴿٢﴾
وَأَنَّهُ تَعَالَىٰ جَدُّ رَبِّنَا مَا اتَّخَذَ صَاحِبَةً وَلَا وَلَدًا ﴿٣﴾ وَأَنَّهُ كَانَ
يَقُولُ سَفِيهُنَا عَلَى اللَّهِ شَطَطًا ﴿٤﴾ وَأَنَّا ظَنَنَّا أَن لَّن تَقُولَ الْإِنسُ
وَالْجِنُّ عَلَى اللَّهِ كَذِبًا ﴿٥﴾ وَأَنَّهُ كَانَ رِجَالٌ مِّنَ الْإِنسِ يَعُوذُونَ بِرِجَالٍ
مِّنَ الْجِنِّ فَزَادُوهُمْ رَهَقًا ﴿٦﴾ وَأَنَّهُمْ ظَنُّوا كَمَا ظَنَنتُمْ أَن لَّن يَبْعَثَ
اللَّهُ أَحَدًا ﴿٧﴾ وَأَنَّا لَمَسْنَا السَّمَاءَ فَوَجَدْنَاهَا مُلِئَتْ حَرَسًا
شَدِيدًا وَشُهُبًا ﴿٨﴾ وَأَنَّا كُنَّا نَقْعُدُ مِنْهَا مَقَاعِدَ لِلسَّمْعِ ۖ فَمَن
يَسْتَمِعِ الْآنَ يَجِدْ لَهُ شِهَابًا رَّصَدًا ﴿٩﴾ وَأَنَّا لَا نَدْرِي أَشَرٌّ أُرِيدَ
بِمَن فِي الْأَرْضِ أَمْ أَرَادَ بِهِمْ رَبُّهُمْ رَشَدًا ﴿١٠﴾ وَأَنَّا مِنَّا الصَّالِحُونَ
وَمِنَّا دُونَ ذَٰلِكَ ۖ كُنَّا طَرَائِقَ قِدَدًا ﴿١١﴾ وَأَنَّا ظَنَنَّا أَن لَّن نُّعْجِزَ
اللَّهَ فِي الْأَرْضِ وَلَن نُّعْجِزَهُ هَرَبًا ﴿١٢﴾ وَأَنَّا لَمَّا سَمِعْنَا الْهُدَىٰ
آمَنَّا بِهِ ۖ فَمَن يُؤْمِن بِرَبِّهِ فَلَا يَخَافُ بَخْسًا وَلَا رَهَقًا ﴿١٣﴾

Sura Jinn

(1) Ka ce: “An yiwo min wahayi na cewa, wata jama’a ta aljannu[1] sun saurari (karatun Alkur’ani), sai suka ce: “Lalle mu mun ji Alkur’ani mai ban mamaki

(2) “Yana shiryarwa zuwa ga daidai, saboda haka muka yi imani da shi; ba kuwa za mu haɗa wani da Ubangijinmu ba har abada

(3) “Kuma lalle yadda lamarin yake, girman Ubangijinmu ya ɗaukaka, bai riki wata mata ko wani ɗa ba

(4) “Kuma lalle yadda lamarin yake, wani wawa daga cikinmu ya kasance yana faɗar mummunar ƙarya game da Allah

(5) “Lalle kuma mun yi tsammanin mutum da aljan ba za su taɓa faɗar ƙarya game da Allah ba

(6) “Kuma lalle yadda lamarin yake, wasu mazaje daga mutane sun kasance suna neman tsari daga wasu mazaje na aljannu, saboda haka suka ƙara musu girman kai

(7) “Kuma lalle su sun yi tsammanin-kamar yadda kuka yi tsammani-cewar Allah ba zai tashi kowa ba har abada

(8) “Kuma lalle mu mun nemi hawa sama, sai muka same ta an cika ta da matsanancin tsaro da taurari (masu jifa da garwashi)

(9) “Lalle kuma mun zamanto a da muna hawa wasu wurare nata don yin sauraro[2]; to duk wanda ya nemi yin sauraro a yanzu zai sama wa kansa wani tauraro wanda aka tanada (don jifan sa)

(10) “Kuma lalle mu ba mu sani ba, shin wani sharri ake nufi da waɗanda ke ƙasa, ko kuwa Ubangijinsu Yana nufin su da shiriya ne?

(11) “Lalle daga cikinmu akwai salihai, daga cikinmu kuma akwai waɗanda ba haka suke ba; mun zamanto hanyoyi daban-daban

(12) “Kuma lalle mu mun tabbatar cewa ba za mu gagari Allah ba a bayan ƙasa, ba kuma za mu gagare Shi ba a guje

(13) “Lalle kuma mu lokacin da muka ji Alkur’ani, sai muka yi imani da shi, to duk wanda zai yi imani da Ubangijinsa, to ba zai ji tsoron ƙwara ko zalunci ba[3]

(1) Su ne wasu aljannu da suka saurari karatun Annabi ( ) a wani wuri da ake kira Baɗnu Nakhla, lokacin da yake yi wa sahabbansa sallar asuba.


(2) Watau a da can lokacin jahiliyya aljannu sun saba hawa sama domin sato bayanan sirri daga tattaunawar mala’iku, suna isar da su ga bokaye a ƙasa.

(3) Watau ba za a tauye masa ladansa ba, kuma ba za a ƙara masa wani laifin da bai aikata ba.

وَأَنَّا مِنَّا ٱلْمُسْلِمُونَ وَمِنَّا ٱلْقَٰسِطُونَ ۖ فَمَنْ أَسْلَمَ فَأُو۟لَٰٓئِكَ
تَحَرَّوْا۟ رَشَدًا ﴿١٤﴾ وَأَمَّا ٱلْقَٰسِطُونَ فَكَانُوا۟ لِجَهَنَّمَ حَطَبًا ﴿١٥﴾
وَأَلَّوِ ٱسْتَقَٰمُوا۟ عَلَى ٱلطَّرِيقَةِ لَأَسْقَيْنَٰهُم مَّآءً غَدَقًا ﴿١٦﴾ لِّنَفْتِنَهُمْ
فِيهِ ۚ وَمَن يُعْرِضْ عَن ذِكْرِ رَبِّهِۦ يَسْلُكْهُ عَذَابًا صَعَدًا ﴿١٧﴾ وَأَنَّ
ٱلْمَسَٰجِدَ لِلَّهِ فَلَا تَدْعُوا۟ مَعَ ٱللَّهِ أَحَدًا ﴿١٨﴾ وَأَنَّهُۥ لَمَّا قَامَ عَبْدُ ٱللَّهِ
يَدْعُوهُ كَادُوا۟ يَكُونُونَ عَلَيْهِ لِبَدًا ﴿١٩﴾ قُلْ إِنَّمَآ أَدْعُوا۟ رَبِّى وَلَآ أُشْرِكُ
بِهِۦٓ أَحَدًا ﴿٢٠﴾ قُلْ إِنِّى لَآ أَمْلِكُ لَكُمْ ضَرًّا وَلَا رَشَدًا ﴿٢١﴾ قُلْ إِنِّى
لَن يُجِيرَنِى مِنَ ٱللَّهِ أَحَدٌ وَلَنْ أَجِدَ مِن دُونِهِۦ مُلْتَحَدًا ﴿٢٢﴾ إِلَّا بَلَٰغًا
مِّنَ ٱللَّهِ وَرِسَٰلَٰتِهِۦ ۚ وَمَن يَعْصِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَإِنَّ لَهُۥ نَارَ جَهَنَّمَ
خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ﴿٢٣﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا رَأَوْا۟ مَا يُوعَدُونَ فَسَيَعْلَمُونَ
مَنْ أَضْعَفُ نَاصِرًا وَأَقَلُّ عَدَدًا ﴿٢٤﴾ قُلْ إِنْ أَدْرِىٓ أَقَرِيبٌ مَّا تُوعَدُونَ
أَمْ يَجْعَلُ لَهُۥ رَبِّىٓ أَمَدًا ﴿٢٥﴾ عَٰلِمُ ٱلْغَيْبِ فَلَا يُظْهِرُ عَلَىٰ غَيْبِهِۦٓ
أَحَدًا ﴿٢٦﴾ إِلَّا مَنِ ٱرْتَضَىٰ مِن رَّسُولٍ فَإِنَّهُۥ يَسْلُكُ مِنۢ بَيْنِ
يَدَيْهِ وَمِنْ خَلْفِهِۦ رَصَدًا ﴿٢٧﴾ لِّيَعْلَمَ أَن قَدْ أَبْلَغُوا۟ رِسَٰلَٰتِ
رَبِّهِمْ وَأَحَاطَ بِمَا لَدَيْهِمْ وَأَحْصَىٰ كُلَّ شَىْءٍ عَدَدًۢا ﴿٢٨﴾

(14) “Kuma lalle mu a cikinmu akwai Musulmi, a cikinmu kuma akwai karkatattu; saboda haka duk wanda ya musulunta, to wadannan sun nufi hanyar shiriya
(15) “Amma kuma karkatattu, to sun kasance makamashi ne ga (wutar) Jahannama.”
(16) Da kuwa (mutan Makka) sun daidaita a kan (Musulunci), to lalle da Mun shayar da su ruwa mai yawa
(17) Don Mu jarrabe su game da shi. Duk kuwa wanda ya kau da kai daga ambaton Ubangijinsa(1) to zai saka shi cikin azaba mai wahala
(18)Kuma lalle masallatai na Allah ne, saboda haka kada ku bauta wa wani tare da Allah
(19) Kuma lalle yadda lamarin yake, yayin da Bawan Allah (Annabi Muhammadu) ya tashi yana bauta masa, sai (aljannu) suka kusa su zamo wasu kan wasu don cincirindo a kansa(2)
(20) Ka ce: “Lalle ina bauta wa Ubangijina ne kawai, ba kuwa na tara wani da Shi.”
(21) Kuma ka ce: “Lalle ni ban mallaki kare muku wata cuta ko janyo muku wani alhairi ba.”
(22) Ka ce: “Lalle ni ba wani mai kare ni daga (azabar) Allah, kuma ba zan taba samun wata mafaka in ba tasa ba
(23) “Sai dai isar da aike daga Allah da kuma sakwanninsa. Duk kuwa wadanda suka saba wa Allah da Manzonsa, to lalle suna da wutar Jahannama, suna madawwama a cikinta har abada.”
(24) Har yayin da (kafirai) suka ga abin da ake yi musu alkawari da shi, to ba da dadewa ba za su san wa ya fi raunanan mataimaka da kuma kankantar jama’a
(25) Ka ce: “Ni ban sani ba, shin kusa yake abin da ake yi muku alkawarinsa ko kuwa Ubangijina zai sanya masa zamani mai tsawo?”
(26) “(Shi ne) Masanin gaibu, sannan ba Ya bayyana gaibunsa ga wani
(27) “Sai manzo da ya yarda da shi, shi kuma lalle Yakan sanya masa tsaro ta gabansa da ta bayansa(3)
(28) “Don Ya bayyanar da cewa, hakika sun isar da sakwannin Ubangijinsu, Ya kuma kewaye da (sanin) abin da yake tare da su, Ya kuma kididdige adadin kowane abu.”

(1) Watau ya bijire wa Alkur’ani da wa’azuzzukan da ke cikinsa.
(2) Watau a Badnu Nakhla lokacin da yake tsaye yana karatun Alkur’ani.
(3) Watau ta hanyar sa masa mala’iku masu tsaron sa domin kada shaidanu su samu kusantar sa.


سُورَةُ المُزَّمِّلِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

يَا أَيُّهَا الْمُزَّمِّلُ ﴿١﴾ قُمِ اللَّيْلَ إِلَّا قَلِيلًا ﴿٢﴾ نِّصْفَهُ أَوِ انقُصْ مِنْهُ قَلِيلًا
﴿٣﴾ أَوْ زِدْ عَلَيْهِ وَرَتِّلِ الْقُرْآنَ تَرْتِيلًا ﴿٤﴾ إِنَّا سَنُلْقِي عَلَيْكَ قَوْلًا
ثَقِيلًا ﴿٥﴾ إِنَّ نَاشِئَةَ اللَّيْلِ هِيَ أَشَدُّ وَطْئًا وَأَقْوَمُ قِيلًا ﴿٦﴾ إِنَّ لَكَ فِي
النَّهَارِ سَبْحًا طَوِيلًا ﴿٧﴾ وَاذْكُرِ اسْمَ رَبِّكَ وَتَبَتَّلْ إِلَيْهِ تَبْتِيلًا ﴿٨﴾
رَّبُّ الْمَشْرِقِ وَالْمَغْرِبِ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَاتَّخِذْهُ وَكِيلًا ﴿٩﴾ وَاصْبِرْ
عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَاهْجُرْهُمْ هَجْرًا جَمِيلًا ﴿١٠﴾ وَذَرْنِي وَالْمُكَذِّبِينَ
أُولِي النَّعْمَةِ وَمَهِّلْهُمْ قَلِيلًا ﴿١١﴾ إِنَّ لَدَيْنَا أَنكَالًا وَجَحِيمًا ﴿١٢﴾
وَطَعَامًا ذَا غُصَّةٍ وَعَذَابًا أَلِيمًا ﴿١٣﴾ يَوْمَ تَرْجُفُ الْأَرْضُ وَالْجِبَالُ
وَكَانَتِ الْجِبَالُ كَثِيبًا مَّهِيلًا ﴿١٤﴾ إِنَّا أَرْسَلْنَا إِلَيْكُمْ رَسُولًا شَاهِدًا
عَلَيْكُمْ كَمَا أَرْسَلْنَا إِلَىٰ فِرْعَوْنَ رَسُولًا ﴿١٥﴾ فَعَصَىٰ فِرْعَوْنُ الرَّسُولَ
فَأَخَذْنَاهُ أَخْذًا وَبِيلًا ﴿١٦﴾ فَكَيْفَ تَتَّقُونَ إِن كَفَرْتُمْ يَوْمًا
يَجْعَلُ الْوِلْدَانَ شِيبًا ﴿١٧﴾ السَّمَاءُ مُنفَطِرٌ بِهِ ۚ كَانَ وَعْدُهُ مَفْعُولًا
﴿١٨﴾ إِنَّ هَٰذِهِ تَذْكِرَةٌ ۖ فَمَن شَاءَ اتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِ سَبِيلًا ﴿١٩﴾

Sura Muzzammil

(1) Ya kai wannan mai lulluɓa[1]!
(2) Ka yi tsaiwar dare sai ɗan kaɗan (daga cikinsa)
(3) Rabinsa ko kuma ka rage kaɗan daga gare shi
(4) Ko ka ƙara a kansa, ka kuma karanta Alƙur'ani daki-daki
(5) Lalle Mu da sannu za Mu saukar maka da zance mai nauyi[2]
(6) Lalle tsayuwar dare ita ta fi tsananin dacewa (game da nutsuwa), ta kuma fi daidaitar magana[3]
(7) Lalle da rana kana da harkoki masu yawa
(8) Ka kuma ambaci sunan Ubangijinka kuma ka yanke alaƙarka da komai don bautarsa
(9) (Shi ne) Ubangijin mahudar rana da mafaɗar rana, babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi, saboda haka ka riƙe Shi Abin dogara
(10) Kuma ka yi haƙuri a kan abin da suke faɗa, kuma ka ƙaurace musu kyakkyawar ƙauracewa[4]
(11) Ka kuma bar ni da masu ƙaryatawa ma'abota ni'ima, ka kuma ɗan saurara musu
(12) Lalle a wurinmu akwai maruruwa da kuma (wutar) Jahimu
(13) Da kuma abinci mai shaƙewa da kuma azaba mai raɗaɗi
(14) A ranar da ƙasa da duwatsu za su girgiza, duwatsun kuma su kasance rairayi tilis
(15) Lalle Mu Muka aiko muku da Manzo yana mai shaida a kanku kamar yadda Muka aiko wani manzo zuwa ga Fir'auna
(16) Sai Fir'auna ya saɓa wa Manzon, sai Muka kama shi kamu mai tsanani
(17) Ta yaya idan kuka kafirta za ku iya kare kanku daga ranar da za ta mayar da yara ƙanana su zama masu furfura?
(18) Sama za ta kece saboda ita (ranar). Alƙawarinsa ya kasance abin aikatawa ne
(19) Lalle wannan wa'azi ne, saboda haka duk wanda ya ga dama sai ya kama hanya zuwa ga Ubangijinsa

(1) Shi ne Manzon Allah ( ) bayan an saukar masa da wahayin farko a kogon Hira, ya dawo gida a tsorace ya lulluɓa da tufafinsa.
(2) Watau Alƙur'ani da zai yiwo masa wahayinsa.
(3) Watau sallar dare ta fi dacewa da nutsuwar zuciya da taimakawa wajen fahimtar zance daidai.
(4) Watau ƙauracewar da babu cutarwa a cikinta.


إِنَّ رَبَّكَ يَعْلَمُ أَنَّكَ تَقُومُ أَدْنَىٰ مِن ثُلُثَيِ ٱلَّيْلِ وَنِصْفَهُۥ وَثُلُثَهُۥ وَطَآئِفَةٌ
مِّنَ ٱلَّذِينَ مَعَكَ ۚ وَٱللَّهُ يُقَدِّرُ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ ۚ عَلِمَ أَن لَّن تُحْصُوهُ فَتَابَ
عَلَيْكُمْ ۖ فَٱقْرَءُوا۟ مَا تَيَسَّرَ مِنَ ٱلْقُرْءَانِ ۚ عَلِمَ أَن سَيَكُونُ مِنكُم مَّرْضَىٰ
وَءَاخَرُونَ يَضْرِبُونَ فِى ٱلْأَرْضِ يَبْتَغُونَ مِن فَضْلِ ٱللَّهِ وَءَاخَرُونَ
يُقَٰتِلُونَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۖ فَٱقْرَءُوا۟ مَا تَيَسَّرَ مِنْهُ ۚ وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟
ٱلزَّكَوٰةَ وَأَقْرِضُوا۟ ٱللَّهَ قَرْضًا حَسَنًا ۚ وَمَا تُقَدِّمُوا۟ لِأَنفُسِكُم مِّنْ خَيْرٍ تَجِدُوهُ
عِندَ ٱللَّهِ هُوَ خَيْرًا وَأَعْظَمَ أَجْرًا ۚ وَٱسْتَغْفِرُوا۟ ٱللَّهَ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٢٠﴾

سُورَةُ المُدَّثِّرِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلْمُدَّثِّرُ ﴿١﴾ قُمْ فَأَنذِرْ ﴿٢﴾ وَرَبَّكَ فَكَبِّرْ ﴿٣﴾ وَثِيَابَكَ فَطَهِّرْ ﴿٤﴾
وَٱلرُّجْزَ فَٱهْجُرْ ﴿٥﴾ وَلَا تَمْنُن تَسْتَكْثِرُ ﴿٦﴾ وَلِرَبِّكَ فَٱصْبِرْ ﴿٧﴾ فَإِذَا نُقِرَ
فِى ٱلنَّاقُورِ ﴿٨﴾ فَذَٰلِكَ يَوْمَئِذٍ يَوْمٌ عَسِيرٌ ﴿٩﴾ عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ غَيْرُ يَسِيرٍ ﴿١٠﴾
ذَرْنِى وَمَنْ خَلَقْتُ وَحِيدًا ﴿١١﴾ وَجَعَلْتُ لَهُۥ مَالًا مَّمْدُودًا ﴿١٢﴾ وَبَنِينَ
شُهُودًا ﴿١٣﴾ وَمَهَّدتُّ لَهُۥ تَمْهِيدًا ﴿١٤﴾ ثُمَّ يَطْمَعُ أَنْ أَزِيدَ ﴿١٥﴾ كَلَّآ ۖ إِنَّهُۥ
كَانَ لِـَٔايَٰتِنَا عَنِيدًا ﴿١٦﴾ سَأُرْهِقُهُۥ صَعُودًا ﴿١٧﴾ إِنَّهُۥ فَكَّرَ وَقَدَّرَ ﴿١٨﴾

(20) Lalle Ubangijinka Yana sane da cewa kai kana tsayawa ƙasa da kashi biyu cikin uku na dare, da kuma rabinsa, da kuma ɗaya bisa ukunsa, kai da wata jama'ar da take tare da kai. Allah ne kuma Yake ƙaddara dare da rana. Ya san kuma cewa, ba za ku iya ƙididdige (sa'o'insa) ba, don haka sai Ya yafe muku; to sai ku karanta abin da ya sauƙaƙa daga Alƙur'ani. Ya san cewa daga cikinku akwai waɗanda za su kasance marasa lafiya, waɗansu kuma suna tafiya a bayan ƙasa don fatauci suna neman falala daga Allah, waɗansu kuma suna yin yaƙi saboda Allah; to sai ku karanta abin da ya sauƙaƙa daga gare shi (Alƙur'ani). Ku kuma tsayar da salla, ku kuma ba da zakka, kuma ku bai wa Allah rance kyakkyawa[1]. Kuma abin da kuka gabatar wa kanku na wani alheri, to za ku same shi wurin Allah, shi ya fi alheri ya kuma fi girman lada. Ku kuma nemi gafarar Allah; lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai

Sura Muddassir

(1) Ya kai mai lulluɓa[2] (2) Tashi ka yi gargaɗi (3) Kuma ka girmama Ubangijinka (4) Ka kuma tsarkake tufafinka (5) Ka kuma ƙaurace wa (bautar) gumaka (6) Kada kuma ka goranta wa (Ubangijinka) da ganin yawan (ayyukanka na ƙwarai)[3] (7) Ka kuma yi haƙuri game da Ubangijinka (8) To idan an busa ƙaho (9) To wannan ranar rana ce mai tsanani (10) A kan kafirai, ba mai sauƙi ba ce (11) Ka bar Ni da wanda Na halitta shi kaɗai[4] (12) Na kuma yi masa baiwa da dukiya maɗuɗuwa (13) Da kuma 'ya'ya masu halartar (tarurruka tare da shi) (14) Na kuma shimfiɗa masa (kyakkyawar rayuwa) iyakar shinfiɗawa (15) Sannan yake kwaɗayin in ƙara (masa) (16) Faufau! Lalle shi ya kasance mai tsaurin kai ne ga ayoyinmu (17) Ba da daɗewa ba zan ɗora masa (azaba) mai matsananciyar wahala (18) Lalle shi ya yi tunani, ya kuma auna (a ransa)

(1) Watau su ciyar da dukiyoyinsu don Allah wuraren da suka dace.

(2) Shi ne Annabi ( ) wanda ya lulluɓa da tufafinsa don tsoron mala'ikan da ya yi idon huɗu da shi a karon farko a kogon Hira.

(3) Watau kada yawansu ya ruɗe shi har ya yi rauni wajen tsayuwa da ayyukan da'awa.

(4) Watau a cikin mahaifiyarsa ba tare da dukiya ko 'ya'ya ba. Shi ne Al-Walidu ɗan Mugira wanda ya addabi Annabi ( ).

فَقُتِلَ كَيْفَ قَدَّرَ ﴿١٩﴾ ثُمَّ قُتِلَ كَيْفَ قَدَّرَ ﴿٢٠﴾ ثُمَّ نَظَرَ ﴿٢١﴾ ثُمَّ عَبَسَ وَبَسَرَ
﴿٢٢﴾ ثُمَّ أَدْبَرَ وَٱسْتَكْبَرَ ﴿٢٣﴾ فَقَالَ إِنْ هَٰذَآ إِلَّا سِحْرٌ يُؤْثَرُ ﴿٢٤﴾ إِنْ هَٰذَآ
إِلَّا قَوْلُ ٱلْبَشَرِ ﴿٢٥﴾ سَأُصْلِيهِ سَقَرَ ﴿٢٦﴾ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا سَقَرُ ﴿٢٧﴾
لَا تُبْقِي وَلَا تَذَرُ ﴿٢٨﴾ لَوَّاحَةٌ لِّلْبَشَرِ ﴿٢٩﴾ عَلَيْهَا تِسْعَةَ عَشَرَ ﴿٣٠﴾ وَمَا جَعَلْنَآ
أَصْحَٰبَ ٱلنَّارِ إِلَّا مَلَٰٓئِكَةً ۙ وَمَا جَعَلْنَا عِدَّتَهُمْ إِلَّا فِتْنَةً لِّلَّذِينَ كَفَرُوا۟
لِيَسْتَيْقِنَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ وَيَزْدَادَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِيمَٰنًا وَلَا يَرْتَابَ
ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْمُؤْمِنُونَ وَلِيَقُولَ ٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ
وَٱلْكَٰفِرُونَ مَاذَآ أَرَادَ ٱللَّهُ بِهَٰذَا مَثَلًا ۚ كَذَٰلِكَ يُضِلُّ ٱللَّهُ مَن يَشَآءُ
وَيَهْدِى مَن يَشَآءُ ۚ وَمَا يَعْلَمُ جُنُودَ رَبِّكَ إِلَّا هُوَ ۚ وَمَا هِىَ إِلَّا ذِكْرَىٰ
لِلْبَشَرِ ﴿٣١﴾ كَلَّا وَٱلْقَمَرِ ﴿٣٢﴾ وَٱلَّيْلِ إِذْ أَدْبَرَ ﴿٣٣﴾ وَٱلصُّبْحِ إِذَآ أَسْفَرَ ﴿٣٤﴾ إِنَّهَا
لَإِحْدَى ٱلْكُبَرِ ﴿٣٥﴾ نَذِيرًا لِّلْبَشَرِ ﴿٣٦﴾ لِمَن شَآءَ مِنكُمْ أَن يَتَقَدَّمَ أَوْ يَتَأَخَّرَ
﴿٣٧﴾ كُلُّ نَفْسٍۭ بِمَا كَسَبَتْ رَهِينَةٌ ﴿٣٨﴾ إِلَّآ أَصْحَٰبَ ٱلْيَمِينِ ﴿٣٩﴾ فِى جَنَّٰتٍ
يَتَسَآءَلُونَ ﴿٤٠﴾ عَنِ ٱلْمُجْرِمِينَ ﴿٤١﴾ مَا سَلَكَكُمْ فِى سَقَرَ ﴿٤٢﴾ قَالُوا۟ لَمْ نَكُ
مِنَ ٱلْمُصَلِّينَ ﴿٤٣﴾ وَلَمْ نَكُ نُطْعِمُ ٱلْمِسْكِينَ ﴿٤٤﴾ وَكُنَّا نَخُوضُ مَعَ
ٱلْخَآئِضِينَ ﴿٤٥﴾ وَكُنَّا نُكَذِّبُ بِيَوْمِ ٱلدِّينِ ﴿٤٦﴾ حَتَّىٰٓ أَتَىٰنَا ٱلْيَقِينُ ﴿٤٧﴾

(19) Sai aka la'ane shi, yaya ya yi irin wannan awon?
(20) Sannan aka kuma la'antar sa, yaya ya yi wannan awon?
(21) Sannan ya yi nazari
(22) Sannan ya ɗaure fuska, ya kuma murtuke
(23) Sannan ya ba da baya (daga imani) ya kuma yi girman kai
(24) Sai ya ce: "Wannan (Alƙur'ani) ba komai ba ne sai sihiri da aka samo (daga wasu)
(25) "Wannan ba komai ba ne sai magana irin ta mutane."
(26) (Allah ya ce): Da sannu zan shigar da shi (wutar) Saƙara
(27) Me ya sanar da kai abin da ake ce wa Saƙara?
(28) Ba ta ragewa kuma ba ta barin (komai) (29) Mai ɗaɗɗaye fata ce
(30) Akwai (mala'iku) goma sha tara suna tsaron ta (31) Ba Mu kuwa sanya masu tsaron wutar ba sai mala'iku, ba Mu kuma sanya adadinsu ba sai don fitina ga waɗanda suka kafirta, don kuma waɗanda aka bai wa littafi su sami yaƙini, waɗanda kuma suka yi imani su ƙara imani, waɗanda aka bai wa littafi da muminai kuma kada su yi tababa, don kuma waɗanda suke da raunin imani a zukatansu da kuma kafirai su ce: "Me Allah Yake nufi da yin misali da wannan (adadin)?" Kamar haka Allah Yake ɓatar da wanda Ya ga dama, Yake kuma shiryar da wanda Ya ga dama. Ba kuma wanda ya san (yawan) rundunar Ubangijinka sai Shi. Ita (Saƙara) kuma ba wata abu ba ce face wa'azi ga mutane (32) A'a. Na rantse da wata (33) Da kuma dare idan ya ba da baya (34) Da kuma asuba idan ta bayyana (da haskenta) (35) Lalle ita (Saƙara) tana ɗaya daga manya-manyan (bala'o'i) (36) Gargaɗi ce ga mutane (37) Ga wanda ya ga dama daga cikinku, ya ci gaba ko ya ci baya (38) Kowane rai jingina ne ga abin da ya tsuwurwurta(1) (39) Sai dai ga ma'abota dama(2) (40) (Su kam suna) cikin gidajen Aljanna suna tambayar juna (41) Game da manyan masu laifuka (42) (Suna cewa): "Me ya shigar da ku cikin Saƙara?"
(43) Suka ce: "Ba mu zama daga cikin masallata ba (44) "Kuma ba mu kasance muna ciyar da miskini ba (45) "Mun kuma kasance muna kutsawa (cikin ɓarna)(3) tare da masu kutsawa (46) "Kuma mun kasance muna ƙaryata ranar sakamako (47) "Har mutuwa ta zo mana."

(1) Watau jingina ne ga ayyukansu, ko dai su hallakar da shi ko su kuɓutar da shi, su 'yanta shi.
(2) Watau waɗanda za su karɓi littattafan ayyukansu ta hannayensu na dama.
(3) Watau suna faɗar ƙarerayi game da Annabi ( ) da Alƙur'ani.

فَمَا تَنفَعُهُمْ شَفَٰعَةُ ٱلشَّٰفِعِينَ ﴿٤٨﴾ فَمَا لَهُمْ عَنِ ٱلتَّذْكِرَةِ مُعْرِضِينَ
﴿٤٩﴾ كَأَنَّهُمْ حُمُرٌ مُّسْتَنفِرَةٌ ﴿٥٠﴾ فَرَّتْ مِن قَسْوَرَةٍۭ ﴿٥١﴾ بَلْ يُرِيدُ
كُلُّ ٱمْرِئٍ مِّنْهُمْ أَن يُؤْتَىٰ صُحُفًا مُّنَشَّرَةً ﴿٥٢﴾ كَلَّاۖ بَل لَّا يَخَافُونَ
ٱلْءَاخِرَةَ ﴿٥٣﴾ كَلَّآ إِنَّهُۥ تَذْكِرَةٌ ﴿٥٤﴾ فَمَن شَآءَ ذَكَرَهُۥ ﴿٥٥﴾ وَمَا يَذْكُرُونَ
إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ هُوَ أَهْلُ ٱلتَّقْوَىٰ وَأَهْلُ ٱلْمَغْفِرَةِ ﴿٥٦﴾

سُورَةُ القِيَامَةِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

لَآ أُقْسِمُ بِيَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ ﴿١﴾ وَلَآ أُقْسِمُ بِٱلنَّفْسِ ٱللَّوَّامَةِ ﴿٢﴾ أَيَحْسَبُ
ٱلْإِنسَٰنُ أَلَّن نَّجْمَعَ عِظَامَهُۥ ﴿٣﴾ بَلَىٰ قَٰدِرِينَ عَلَىٰٓ أَن نُّسَوِّيَ بَنَانَهُۥ ﴿٤﴾ بَلْ
يُرِيدُ ٱلْإِنسَٰنُ لِيَفْجُرَ أَمَامَهُۥ ﴿٥﴾ يَسْـَٔلُ أَيَّانَ يَوْمُ ٱلْقِيَٰمَةِ ﴿٦﴾ فَإِذَا بَرِقَ
ٱلْبَصَرُ ﴿٧﴾ وَخَسَفَ ٱلْقَمَرُ ﴿٨﴾ وَجُمِعَ ٱلشَّمْسُ وَٱلْقَمَرُ ﴿٩﴾ يَقُولُ ٱلْإِنسَٰنُ
يَوْمَئِذٍ أَيْنَ ٱلْمَفَرُّ ﴿١٠﴾ كَلَّا لَا وَزَرَ ﴿١١﴾ إِلَىٰ رَبِّكَ يَوْمَئِذٍ ٱلْمُسْتَقَرُّ ﴿١٢﴾ يُنَبَّؤُا۟
ٱلْإِنسَٰنُ يَوْمَئِذٍۭ بِمَا قَدَّمَ وَأَخَّرَ ﴿١٣﴾ بَلِ ٱلْإِنسَٰنُ عَلَىٰ نَفْسِهِۦ بَصِيرَةٌ ﴿١٤﴾
وَلَوْ أَلْقَىٰ مَعَاذِيرَهُۥ ﴿١٥﴾ لَا تُحَرِّكْ بِهِۦ لِسَانَكَ لِتَعْجَلَ بِهِۦٓ ﴿١٦﴾ إِنَّ عَلَيْنَا
جَمْعَهُۥ وَقُرْءَانَهُۥ ﴿١٧﴾ فَإِذَا قَرَأْنَٰهُ فَٱتَّبِعْ قُرْءَانَهُۥ ﴿١٨﴾ ثُمَّ إِنَّ عَلَيْنَا بَيَانَهُۥ ﴿١٩﴾

(48) Saboda haka ceton masu ceto ba zai amfane su ba
(49) To me ya same su ne suke bijire wa wa'azi?
(50) Kai ka ce su jakunan jeji ne da aka firgitar
(51) Da suka guje wa zaki
(52) A'a, kowane mutum daga cikinsu yana so ne a ba shi takardu buɗaɗɗu[1] (kafin su bi Annabi)
(53) Faufau! A'a, su dai ba sa tsoron ranar lahira ne
(54) Tabbas, lalle shi (Alƙur'ani) wa'azi ne
(55) To duk wanda ya ga dama sai ya wa'azantu
(56) Ba sa kuma wa'azantuwa sai idan Allah Ya ga dama. Shi ne Ya cancanci taƙawa, kuma Shi ne Ya cancanci yin gafara

Sura Kiyama

(1) Ina rantsuwa da ranar alƙiyama (2) Ina kuma rantsuwa da rai mai yawan zargin (kansa)[2] (3) Yanzu mutum yana tsammanin ba za Mu tattara ƙasusuwansa ba? (4) E, (Mu) Masu iko ne a kan Mu daidaita gaɓoɓin yatsunsa (5) Ba haka ba ne, mutum yana nufi ne kawai ya gurɓata gabansa (da saɓon Allah) (6) Yana tambaya yaushe ne ranar alƙiyamar? (7) To lokacin da gani ya ruɗe (8) Wata kuma ya yi duhu (9) Aka kuma haɗe rana da wata (a mafitarsu) (10) A wannan rana ne mutum zai ce: "Ina wurin gudu?" (11) Faufau, babu mafaka (12) Zuwa ga Ubangijinka ne kawai matabbata take a wannan rana (13) Za a bai wa mutum labari a wannan rana na abin da ya gabatar da kuma (abin da) ya jinkirtar (na ayyukansa) (14) A'a, shi dai mutum mai shaida ne a kan kansa (15) Ko da kuwa ya kawo uzururrukansa (16) (Allah ya ce da Annabinsa): Kada ka motsa harshenka da shi (Alƙur'ani) don gaggauta (karanta) shi (17) Lalle tattara shi (a zuciyarka) da karanta shi yana kanmu (18) Saboda haka idan Muka karanta (maka) shi sai ka bi karatunsa (19) Sannan kuma bayaninsa yana kanmu

(1) Watau a ba shi buɗaɗɗen littafi wanda zai ba shi labari cewa Annabi Muhammadu ( ) Manzon Allah ne.

(2) Watau a kan gazawarsa wajen ayyukan alheri ko a kan aikata laifuka.

كَلَّا بَلْ تُحِبُّونَ ٱلْعَاجِلَةَ ﴿٢٠﴾ وَتَذَرُونَ ٱلْآخِرَةَ ﴿٢١﴾ وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ نَّاضِرَةٌ
﴿٢٢﴾ إِلَىٰ رَبِّهَا نَاظِرَةٌ ﴿٢٣﴾ وَوُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ بَاسِرَةٌ ﴿٢٤﴾ تَظُنُّ أَن يُفْعَلَ بِهَا
فَاقِرَةٌ ﴿٢٥﴾ كَلَّآ إِذَا بَلَغَتِ ٱلتَّرَاقِيَ ﴿٢٦﴾ وَقِيلَ مَنْ ۜ رَاقٍ ﴿٢٧﴾ وَظَنَّ أَنَّهُ ٱلْفِرَاقُ
﴿٢٨﴾ وَٱلْتَفَّتِ ٱلسَّاقُ بِٱلسَّاقِ ﴿٢٩﴾ إِلَىٰ رَبِّكَ يَوْمَئِذٍ ٱلْمَسَاقُ ﴿٣٠﴾ فَلَا
صَدَّقَ وَلَا صَلَّىٰ ﴿٣١﴾ وَلَٰكِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰ ﴿٣٢﴾ ثُمَّ ذَهَبَ إِلَىٰٓ أَهْلِهِۦ يَتَمَطَّىٰٓ
﴿٣٣﴾ أَوْلَىٰ لَكَ فَأَوْلَىٰ ﴿٣٤﴾ ثُمَّ أَوْلَىٰ لَكَ فَأَوْلَىٰٓ ﴿٣٥﴾ أَيَحْسَبُ ٱلْإِنسَٰنُ
أَن يُتْرَكَ سُدًى ﴿٣٦﴾ أَلَمْ يَكُ نُطْفَةً مِّن مَّنِىٍّ يُمْنَىٰ ﴿٣٧﴾ ثُمَّ كَانَ
عَلَقَةً فَخَلَقَ فَسَوَّىٰ ﴿٣٨﴾ فَجَعَلَ مِنْهُ ٱلزَّوْجَيْنِ ٱلذَّكَرَ
وَٱلْأُنثَىٰٓ ﴿٣٩﴾ أَلَيْسَ ذَٰلِكَ بِقَٰدِرٍ عَلَىٰٓ أَن يُحْۦِىَ ٱلْمَوْتَىٰ ﴿٤٠﴾

سُورَةُ الْإِنسَانِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

هَلْ أَتَىٰ عَلَى ٱلْإِنسَٰنِ حِينٌ مِّنَ ٱلدَّهْرِ لَمْ يَكُن شَيْـًٔا مَّذْكُورًا ﴿١﴾ إِنَّا خَلَقْنَا
ٱلْإِنسَٰنَ مِن نُّطْفَةٍ أَمْشَاجٍ نَّبْتَلِيهِ فَجَعَلْنَٰهُ سَمِيعًۢا بَصِيرًا ﴿٢﴾ إِنَّا
هَدَيْنَٰهُ ٱلسَّبِيلَ إِمَّا شَاكِرًا وَإِمَّا كَفُورًا ﴿٣﴾ إِنَّآ أَعْتَدْنَا لِلْكَٰفِرِينَ سَلَٰسِلَا۠
وَأَغْلَٰلًا وَسَعِيرًا ﴿٤﴾ إِنَّ ٱلْأَبْرَارَ يَشْرَبُونَ مِن كَأْسٍ كَانَ مِزَاجُهَا كَافُورًا ﴿٥﴾

(20) Haba, ku dai kawai kuna son duniya ne
(21) Kuna kuma barin lahira
(22) Wasu fuskokin a wannan rana a ni'imce suke
(23) Suna masu kallon Ubangijinsu
(24) Wasu fuskokin kuma a wannan rana a ɗaɗɗaure suke
(25) Suna tabbatar da cewa, za a saukar musu da wani bala'i
(26) Ku saurara, yayin da rai ya iso a karankarama[1]
(27) Aka kuma ce: "Wane ne mai tawaida[2]?"
(28) Ya kuma tabbata cewar (wannan) shi ne rabuwarsa (da duniya)
(29) Kuma tsananin bala'i ya haɗu (30) To zuwa Ubangijinka ne (za a) kora ka a wannan ranar (31) To bai ba da gaskiya ba bai kuma yi salla ba (32) Sai dai ya ƙaryata ya kuma ba da baya (33) Sannan ya tafi zuwa ga iyalinsa yana taƙama (34) (Azaba) ta doso ka, ta fa doso ka!
(35) Sannan ta doso ka, ta fa doso ka! (36) Yanzu mutum yana tsammanin za a bar shi haka sasaka[3]? (37) Shin bai kasance wani ɗigo na maniyyi da ake zuba shi (a mahaifa) ba? (38) Sannan ya zama gudan jini sannan (Allah) Ya halicce (shi) sai Ya daidaita (shi)? (39) Sannan Ya halicci dangi biyu daga gare shi, namiji da mace? (40) Yanzu wannan bai zama Mai iko a kan ya raya matattu ba?

Sura Insan

(1) Haƙiƙa wani yanki na zamani ya zo wa mutum yayin da bai zama wani abin ambato ba[4] (2) Lalle Mun halicci mutum daga maniyyi gamin-gambiza[5] don Mu jarrabe shi, sai Muka sanya shi mai ji mai gani (3) Lalle Mun bayyana masa hanya, ko dai (ya zama) mai godewa ko kuma mai butulcewa (4) Lalle Mun tanadar wa kafirai sarƙoƙi da ƙuƙumai da wutar Sa'ira (5) Lalle mutane nagari suna sha daga wani kofin (giya) da mahaɗinta ya kasance kafur ne[6]

(1) Watau ya zo ƙasusuwan ƙirji a lokacin gargarar mutuwa.

(2) Watau masu jinya su riƙa tambayar junansu cewa, wane ne zai yi masa ruƙya ko zai zamu sauƙi?

(3) Watau za a ƙyale shi ya yi abin da ya ga dama ba tare da umarni ko hani ba?

(4) Watau babu shi gaba ɗaya, babu kuma wanda ya san shi.

(5) Watau tsakanin na namiji da na mace.

(6) Watau mai daɗin ƙamshi.

عَيۡنٗا يَشۡرَبُ بِهَا عِبَادُ ٱللَّهِ يُفَجِّرُونَهَا تَفۡجِيرٗا ٦ يُوفُونَ بِٱلنَّذۡرِ وَيَخَافُونَ
يَوۡمٗا كَانَ شَرُّهُۥ مُسۡتَطِيرٗا ٧ وَيُطۡعِمُونَ ٱلطَّعَامَ عَلَىٰ حُبِّهِۦ مِسۡكِينٗا
وَيَتِيمٗا وَأَسِيرًا ٨ إِنَّمَا نُطۡعِمُكُمۡ لِوَجۡهِ ٱللَّهِ لَا نُرِيدُ مِنكُمۡ جَزَآءٗ وَلَا شُكُورًا
٩ إِنَّا نَخَافُ مِن رَّبِّنَا يَوۡمًا عَبُوسٗا قَمۡطَرِيرٗا ١٠ فَوَقَىٰهُمُ ٱللَّهُ شَرَّ ذَٰلِكَ
ٱلۡيَوۡمِ وَلَقَّىٰهُمۡ نَضۡرَةٗ وَسُرُورٗا ١١ وَجَزَىٰهُم بِمَا صَبَرُواْ جَنَّةٗ وَحَرِيرٗا ١٢
مُّتَّكِـِٔينَ فِيهَا عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِۖ لَا يَرَوۡنَ فِيهَا شَمۡسٗا وَلَا زَمۡهَرِيرٗا ١٣
وَدَانِيَةً عَلَيۡهِمۡ ظِلَٰلُهَا وَذُلِّلَتۡ قُطُوفُهَا تَذۡلِيلٗا ١٤ وَيُطَافُ عَلَيۡهِم بِـَٔانِيَةٖ
مِّن فِضَّةٖ وَأَكۡوَابٖ كَانَتۡ قَوَارِيرَا۠ ١٥ قَوَارِيرَا۟ مِن فِضَّةٖ قَدَّرُوهَا تَقۡدِيرٗا ١٦
وَيُسۡقَوۡنَ فِيهَا كَأۡسٗا كَانَ مِزَاجُهَا زَنجَبِيلًا ١٧ عَيۡنٗا فِيهَا تُسَمَّىٰ سَلۡسَبِيلٗا
١٨ ۞ وَيَطُوفُ عَلَيۡهِمۡ وِلۡدَٰنٞ مُّخَلَّدُونَ إِذَا رَأَيۡتَهُمۡ حَسِبۡتَهُمۡ لُؤۡلُؤٗا مَّنثُورٗا
١٩ وَإِذَا رَأَيۡتَ ثَمَّ رَأَيۡتَ نَعِيمٗا وَمُلۡكٗا كَبِيرًا ٢٠ عَٰلِيَهُمۡ ثِيَابُ سُندُسٍ
خُضۡرٞ وَإِسۡتَبۡرَقٞۖ وَحُلُّوٓاْ أَسَاوِرَ مِن فِضَّةٖ وَسَقَىٰهُمۡ رَبُّهُمۡ شَرَابٗا
طَهُورًا ٢١ إِنَّ هَٰذَا كَانَ لَكُمۡ جَزَآءٗ وَكَانَ سَعۡيُكُم مَّشۡكُورًا ٢٢ إِنَّا
نَحۡنُ نَزَّلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡقُرۡءَانَ تَنزِيلٗا ٢٣ فَٱصۡبِرۡ لِحُكۡمِ رَبِّكَ وَلَا تُطِعۡ
مِنۡهُمۡ ءَاثِمًا أَوۡ كَفُورٗا ٢٤ وَٱذۡكُرِ ٱسۡمَ رَبِّكَ بُكۡرَةٗ وَأَصِيلٗا ٢٥

(6) Wani marmaro ne da bayin Allah suke sha daga gare shi suna ɓuɓɓugo shi ɓuɓɓugowa ta haƙiƙa
(7) Suna cika alƙawari na bakance suna kuma tsoron ranar da sharrinta ya kasance mai bazuwa ne
(8) Suna kuma ciyar da abinci tare da suna son sa ga miskini da maraya da kuma ribataccen yaƙi
(9) (Suna cewa): "Mu kawai muna ciyar da ku ne saboda Allah, ba ma nufin sakamako ko godiya daga wurinka
(10) "Lalle mu muna jin tsoron rana mai sa ɗaure fuska, matsananciya daga

Ubangijinmu (11) Sai Allah Ya kare su (daga) sharrin wannan ranar Ya kuma ba su haske (a fuskokinsu) da kuma farin ciki (12) Ya kuma saka musu da Aljanna da alharini saboda haƙurin da suka yi (13) Suna masu kishingiɗa a cikinta a kan gadaje; ba sa ganin rana ko jin tsananin sanyi a cikinta (14) Inuwoyinta kuma suna kusa da su, an kuma hore musu 'ya'yan itatuwanta matuƙar horewa (15) Ana kuma kai-kawo a tsakaninsu da ƙorai na azurfa da kofuna waɗanda suka kasance na ƙarau (16) Karau ɗin na azurfa ne, sun auna su, aunawa daidai da buƙata
(17) Ana kuma shayar da su wata giya a cikinta, wadda mahaɗinta ya kasance citta mai yatsu ce (18) Wani marmaro ne a cikinta da ake kiran sa Salsabilu (19) Samari hadimai dawwamammu (da ba sa tsufa) kuma suna kai-kawo tsakaninsu, idan ka gan su sai ka yi tsammanin su wani lu'ulu'u ne da aka baza (20) Idan kuma ka yi kallo a can, za ka ga ni'ima da kuma mulki ƙasaitacce (21) Suna sanye da korayen tufafin alharini marar kauri da na alharini mai kauri; aka kuma yi musu ado da warawarai na azurfa, Ubangijinsu kuma Ya shayar da su abin sha mai tsarki (22) Lalle wannan ya kasance sakamako ne a gare ku, kuma aikinku ya kasance abin godewa (23) Lalle Mu Muka saukar maka da Alƙur'ani daki-daki (24) Saboda haka ka yi haƙuri da hukuncin Ubangijinka kada kuwa ka bi mai yawan saɓo ko mai yawan kafircewa daga cikinsu (25) Ka kuma ambaci sunan Ubangijinka safe da yamma

وَمِنَ ٱلَّيۡلِ فَٱسۡجُدۡ لَهُۥ وَسَبِّحۡهُ لَيۡلٗا طَوِيلًا ٢٦ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ
يُحِبُّونَ ٱلۡعَاجِلَةَ وَيَذَرُونَ وَرَآءَهُمۡ يَوۡمٗا ثَقِيلٗا ٢٧ نَّحۡنُ خَلَقۡنَٰهُمۡ
وَشَدَدۡنَآ أَسۡرَهُمۡۖ وَإِذَا شِئۡنَا بَدَّلۡنَآ أَمۡثَٰلَهُمۡ تَبۡدِيلًا ٢٨ إِنَّ
هَٰذِهِۦ تَذۡكِرَةٞۖ فَمَن شَآءَ ٱتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ سَبِيلٗا ٢٩ وَمَا تَشَآءُونَ
إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمٗا ٣٠ يُدۡخِلُ
مَن يَشَآءُ فِي رَحۡمَتِهِۦۚ وَٱلظَّٰلِمِينَ أَعَدَّ لَهُمۡ عَذَابًا أَلِيمَۢا ٣١

سُورَةُ المُرسَلَاتِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلۡمُرۡسَلَٰتِ عُرۡفٗا ١ فَٱلۡعَٰصِفَٰتِ عَصۡفٗا ٢ وَٱلنَّٰشِرَٰتِ نَشۡرٗا ٣
فَٱلۡفَٰرِقَٰتِ فَرۡقٗا ٤ فَٱلۡمُلۡقِيَٰتِ ذِكۡرًا ٥ عُذۡرًا أَوۡ نُذۡرًا ٦ إِنَّمَا
تُوعَدُونَ لَوَٰقِعٞ ٧ فَإِذَا ٱلنُّجُومُ طُمِسَتۡ ٨ وَإِذَا ٱلسَّمَآءُ فُرِجَتۡ
٩ وَإِذَا ٱلۡجِبَالُ نُسِفَتۡ ١٠ وَإِذَا ٱلرُّسُلُ أُقِّتَتۡ ١١ لِأَيِّ يَوۡمٍ أُجِّلَتۡ
١٢ لِيَوۡمِ ٱلۡفَصۡلِ ١٣ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا يَوۡمُ ٱلۡفَصۡلِ ١٤ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ
لِّلۡمُكَذِّبِينَ ١٥ أَلَمۡ نُهۡلِكِ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٦ ثُمَّ نُتۡبِعُهُمُ ٱلۡأٓخِرِينَ
١٧ كَذَٰلِكَ نَفۡعَلُ بِٱلۡمُجۡرِمِينَ ١٨ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ١٩

(26) Da daddare kuma sai ka yi sujjada a gare Shi, ka kuma yi nafiloli saboda Shi a tsawon dare
(27) Lalle waɗannan suna son mai gaggawar ƙarewa (watau duniya), suna kuma watsi da rana mai nauyi(1) a bayansu
(28) Mu Muka halicce su Muka kuma ƙarfafa gaɓoɓinsu; idan kuwa Muka ga dama sai Mu musanya irinsu (kyakkyawar) musanyawa
(29) Lalle wannan wa'azi ne; saboda haka wanda ya ga dama sai ya riƙi hanya zuwa ga Ubangijinsa
(30) Kuma ba ganin damarku ba ce sai abin da Allah ya ga dama. Lalle Allah Ya kasance Masani, Mai hikima
(31) Yana shigar da wanda Ya ga dama cikin rahamarsa. Azzalumai kuwa Ya tanadar musu azaba mai raɗaɗi

Sura Mursalat

(1) Na rantse da iska mai bibiyar juna (2) Da kuma iska mai tasowa da tsanani (3) Da iska mai watso ruwa watsowa (4) Da kuma (mala'iku) masu rarrabe ƙarya da gaskiya iya rarrabewa (5) Sannan masu sauko da wahayi (6) Don yanke hanzari ko don gargaɗi (7) Lalle abin da ake yi muku alƙawari tabbas mai afkuwa ne (8) To idan taurari aka shafe haskensu (9) Idan kuma sama aka tsattsage ta (10) Idan kuma duwatsu aka sheƙe su (11) Idan kuma manzanni aka tattara su(2) (12) Ga wacce rana ce aka ƙayyaje musu (13) Ga rana ta yin hukunci(3) (14) Me kuma ya sanar da kai ranar yin hukunci (15) Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa (16) Yanzu ba Mu hallakar da na farko ba? (17) Sannan Muka biyo su da na ƙarshe? (18) Kamar haka Muke yi wa masu manyan laifuka (19) Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa

(1) Watau ranar alƙiyama mai cike da wahalhalu da musibu iri-iri.

(2) Watau don su ba da shaida cewa sun isar wa al'ummunnsu saƙon Allah.

(3) Watau hukunci tsakanin bayi, a bayyana mai gaskiya da marar gaskiya da ɗan wuta da ɗan Aljanna.

أَلَمْ نَخْلُقكُّم مِّن مَّآءٍ مَّهِينٍ ﴿٢٠﴾ فَجَعَلْنَٰهُ فِى قَرَارٍ مَّكِينٍ ﴿٢١﴾ إِلَىٰ قَدَرٍ
مَّعْلُومٍ ﴿٢٢﴾ فَقَدَرْنَا فَنِعْمَ ٱلْقَٰدِرُونَ ﴿٢٣﴾ وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿٢٤﴾
أَلَمْ نَجْعَلِ ٱلْأَرْضَ كِفَاتًا ﴿٢٥﴾ أَحْيَآءً وَأَمْوَٰتًا ﴿٢٦﴾ وَجَعَلْنَا فِيهَا رَوَٰسِىَ
شَمِخَٰتٍ وَأَسْقَيْنَٰكُم مَّآءً فُرَاتًا ﴿٢٧﴾ وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿٢٨﴾
ٱنطَلِقُوٓا۟ إِلَىٰ مَا كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ﴿٢٩﴾ ٱنطَلِقُوٓا۟ إِلَىٰ ظِلٍّ ذِى ثَلَٰثِ
شُعَبٍ ﴿٣٠﴾ لَّا ظَلِيلٍ وَلَا يُغْنِى مِنَ ٱللَّهَبِ ﴿٣١﴾ إِنَّهَا تَرْمِى بِشَرَرٍ
كَٱلْقَصْرِ ﴿٣٢﴾ كَأَنَّهُۥ جِمَٰلَتٌ صُفْرٌ ﴿٣٣﴾ وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿٣٤﴾
هَٰذَا يَوْمُ لَا يَنطِقُونَ ﴿٣٥﴾ وَلَا يُؤْذَنُ لَهُمْ فَيَعْتَذِرُونَ ﴿٣٦﴾ وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ
لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿٣٧﴾ هَٰذَا يَوْمُ ٱلْفَصْلِ ۖ جَمَعْنَٰكُمْ وَٱلْأَوَّلِينَ ﴿٣٨﴾ فَإِن كَانَ
لَكُمْ كَيْدٌ فَكِيدُونِ ﴿٣٩﴾ وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿٤٠﴾ إِنَّ ٱلْمُتَّقِينَ
فِى ظِلَٰلٍ وَعُيُونٍ ﴿٤١﴾ وَفَوَٰكِهَ مِمَّا يَشْتَهُونَ ﴿٤٢﴾ كُلُوا۟ وَٱشْرَبُوا۟ هَنِيٓـًٔۢا
بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٤٣﴾ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجْزِى ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٤٤﴾ وَيْلٌ
يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿٤٥﴾ كُلُوا۟ وَتَمَتَّعُوا۟ قَلِيلًا إِنَّكُم مُّجْرِمُونَ ﴿٤٦﴾ وَيْلٌ
يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿٤٧﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱرْكَعُوا۟ لَا يَرْكَعُونَ ﴿٤٨﴾
وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿٤٩﴾ فَبِأَىِّ حَدِيثٍۭ بَعْدَهُۥ يُؤْمِنُونَ ﴿٥٠﴾

(20) Yanzu ba Mu halicce ku daga wani wulaƙantaccen ruwa ba?
(21) Sannan Muka sanya shi cikin matabbata mai aminci?
(22) Zuwa wani lokaci sananne?
(23) Sannan Muka ƙaddara (komai ta yadda ya dace)? To madalla da Masu ƙaddarawa
(24) Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa
(25) Yanzu ba Mu sanya ƙasa (ta zama) matattara ba?
(26) (Ga) rayayyu da matattu[1]?
(27) Muka kuma sanya kafaffun duwatsu dogaye a cikinta, Muka kuma shayar da ku ruwa mai dadi?
(28) Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa
(29) Ku tafi zuwa ga abin da kuka kasance kuna ƙaryatawa
(30) Ku tafi zuwa wata inuwa mai rassa uku
(31) Ba mai ba da inuwa ba kuma ba mai karewa daga harshen wuta ba
(32) Haƙiƙa ita tana jefa tartsatsi kamar ƙaton gini
(33) Kai ka ce su raƙuma ne baƙaƙe
(34) Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa
(35) Wannan ita ce ranar da ba sa magana
(36) Kuma ba za a yi musu izini ba balle su kawo hanzari
(37) Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa
(38) Wannan ita ce rana ta yin hukunci da Muka tara ku da na farko
(39) To idan kuna da wani tanadi na makirci sai ku ƙulla Mini
(40) Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa
(41) Lalle masu taƙawa suna cikin inuwoyi da idanuwan ruwa
(42) Da kuma ababan marmari daga abin da suke sha'awa
(43) Ku ci kuma ku sha kuna masu farin ciki saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa
(44) Lalle Mu kamar haka Muke saka wa masu kyautatawa
(45) Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa
(46) Ku ci kuma ku ji daɗi kaɗan (a duniya), lalle ku kun tabbata manyan masu laifi
(47) Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa
(48) Idan kuma aka ce da su: "Ku yi ruku'u", to ba za su yi ruku'u ba
(49) Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa
(50) To da wane irin zance ne bayansa (Alƙur'ani) za su yi imani?

(1) Watau masu rai a cikin gidajensu a bayanta, matatu kuma a binne a cikin ƙaburburansu a ƙarƙashinta.

سُورَةُ النَّبَإِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

عَمَّ يَتَسَاءَلُونَ ﴿١﴾ عَنِ النَّبَإِ الْعَظِيمِ ﴿٢﴾ الَّذِي هُمْ فِيهِ مُخْتَلِفُونَ ﴿٣﴾
كَلَّا سَيَعْلَمُونَ ﴿٤﴾ ثُمَّ كَلَّا سَيَعْلَمُونَ ﴿٥﴾ أَلَمْ نَجْعَلِ الْأَرْضَ مِهَادًا ﴿٦﴾
وَالْجِبَالَ أَوْتَادًا ﴿٧﴾ وَخَلَقْنَاكُمْ أَزْوَاجًا ﴿٨﴾ وَجَعَلْنَا نَوْمَكُمْ سُبَاتًا
﴿٩﴾ وَجَعَلْنَا اللَّيْلَ لِبَاسًا ﴿١٠﴾ وَجَعَلْنَا النَّهَارَ مَعَاشًا ﴿١١﴾ وَبَنَيْنَا
فَوْقَكُمْ سَبْعًا شِدَادًا ﴿١٢﴾ وَجَعَلْنَا سِرَاجًا وَهَّاجًا ﴿١٣﴾ وَأَنْزَلْنَا مِنَ
الْمُعْصِرَاتِ مَاءً ثَجَّاجًا ﴿١٤﴾ لِنُخْرِجَ بِهِ حَبًّا وَنَبَاتًا ﴿١٥﴾ وَجَنَّاتٍ
أَلْفَافًا ﴿١٦﴾ إِنَّ يَوْمَ الْفَصْلِ كَانَ مِيقَاتًا ﴿١٧﴾ يَوْمَ يُنفَخُ فِي الصُّورِ
فَتَأْتُونَ أَفْوَاجًا ﴿١٨﴾ وَفُتِحَتِ السَّمَاءُ فَكَانَتْ أَبْوَابًا ﴿١٩﴾ وَسُيِّرَتِ
الْجِبَالُ فَكَانَتْ سَرَابًا ﴿٢٠﴾ إِنَّ جَهَنَّمَ كَانَتْ مِرْصَادًا ﴿٢١﴾ لِّلطَّاغِينَ
مَآبًا ﴿٢٢﴾ لَّابِثِينَ فِيهَا أَحْقَابًا ﴿٢٣﴾ لَّا يَذُوقُونَ فِيهَا بَرْدًا وَلَا شَرَابًا
﴿٢٤﴾ إِلَّا حَمِيمًا وَغَسَّاقًا ﴿٢٥﴾ جَزَاءً وِفَاقًا ﴿٢٦﴾ إِنَّهُمْ كَانُوا
لَا يَرْجُونَ حِسَابًا ﴿٢٧﴾ وَكَذَّبُوا بِآيَاتِنَا كِذَّابًا ﴿٢٨﴾ وَكُلَّ شَيْءٍ
أَحْصَيْنَاهُ كِتَابًا ﴿٢٩﴾ فَذُوقُوا فَلَن نَّزِيدَكُمْ إِلَّا عَذَابًا ﴿٣٠﴾

Sura Naba’i

(1) Game da me suke tambayar junansu?
(2) Game da labari ne mai girma[1]
(3) Wanda game da shi ne suke sabani
(4) Ba haka ne ba, da sannu za su sani[2]
(5) Sannan kuma tabbas, da sannu za su sani
(6) Yanzu ba mu sanya ƙasa shimfiɗa ba?
(7) Duwatsu kuma turaku?
(8) Muka kuma halicce ku bibbiyu (watau maza da mata)?
(9) Muka kuma sanya baccinku (ya zama) hutu?
(10) Muka kuma sanya dare (ya zama) sutura[3]?
(11) Muka kuma sanya yini don neman abinci?
(12) Muka kuma gina (sammai) bakwai ƙarfafa a sama da ku?
(13) Muka kuma sanya wata fitila mai tsananin haske (watau rana)?
(14) Muka kuma saukar da ruwa mai kwarara daga (hadari) da ya batse da ruwa?
(15) Domin Mu fitar da ƙwayoyi da tsirrai da shi?
(16) Da kuma gonaki masu itatuwa sassarƙe da juna?
(17) Lalle ranar hukunci ta kasance (rana ce) mai tsayayyen lokaci
(18) Ranar da za a busa ƙaho[4] sai ku zo jama’a-jama’a
(19) Aka kuma buɗe sama sai ta zama ƙofofi[5]
(20) Aka kuma tafiyar da duwatsu sai suka zama kawalwalniya
(21) Lalle Jahannama ta kasance madakata ce
(22) Makoma ce ga masu ɗagawa
(23) Masu zama ne a cikinta shekaru aru-aru
(24) Ba sa ɗanɗanar wani sanyi a cikinta ko wani abin sha
(25) Sai tafasasshen ruwa da ruwan mugunya
(26) Don sakayya da ta dace
(27) Lalle su sun kasance ba sa tsoron hisabi
(28) Suka kuma ƙaryata ayoyinmu iyakar ƙaryatawa
(29) Kuma kowane abu Mun ƙididdige shi a rubuce
(30) (Sai a ce da su): To ku ɗanɗana, don ba za Mu ƙara muku ba sai dai wata azaba.”

(1) Watau Alqur’ani wanda ya qunshi magana a kan ranar alqiyama da za a yi wa mutane hisabi a ciki.
(2) Watau za su san mummunan sakamakon qaryata shi da suke yi.
(3) Watau idan ya lulluve da duhunsa.
(4) Watau busa ta biyu.
(5) Watau inda mala’iku za su yi ta sauka da umarnin Allah.

إِنَّ لِلْمُتَّقِينَ مَفَازًا ﴿٣١﴾ حَدَآئِقَ وَأَعْنَٰبًا ﴿٣٢﴾ وَكَوَاعِبَ أَتْرَابًا ﴿٣٣﴾ وَكَأْسًا
دِهَاقًا ﴿٣٤﴾ لَّا يَسْمَعُونَ فِيهَا لَغْوًا وَلَا كِذَّٰبًا ﴿٣٥﴾ جَزَآءً مِّن رَّبِّكَ عَطَآءً
حِسَابًا ﴿٣٦﴾ رَّبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا ٱلرَّحْمَٰنِ لَا يَمْلِكُونَ
مِنْهُ خِطَابًا ﴿٣٧﴾ يَوْمَ يَقُومُ ٱلرُّوحُ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ صَفًّا لَّا يَتَكَلَّمُونَ
إِلَّا مَنْ أَذِنَ لَهُ ٱلرَّحْمَٰنُ وَقَالَ صَوَابًا ﴿٣٨﴾ ذَٰلِكَ ٱلْيَوْمُ ٱلْحَقُّ فَمَن
شَآءَ ٱتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ مَـَٔابًا ﴿٣٩﴾ إِنَّآ أَنذَرْنَٰكُمْ عَذَابًا قَرِيبًا يَوْمَ يَنظُرُ
ٱلْمَرْءُ مَا قَدَّمَتْ يَدَاهُ وَيَقُولُ ٱلْكَافِرُ يَٰلَيْتَنِى كُنتُ تُرَٰبًۢا ﴿٤٠﴾

سُورَةُ النَّازِعَاتِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلنَّٰزِعَٰتِ غَرْقًا ﴿١﴾ وَٱلنَّٰشِطَٰتِ نَشْطًا ﴿٢﴾ وَٱلسَّٰبِحَٰتِ سَبْحًا ﴿٣﴾
فَٱلسَّٰبِقَٰتِ سَبْقًا ﴿٤﴾ فَٱلْمُدَبِّرَٰتِ أَمْرًا ﴿٥﴾ يَوْمَ تَرْجُفُ ٱلرَّاجِفَةُ ﴿٦﴾
تَتْبَعُهَا ٱلرَّادِفَةُ ﴿٧﴾ قُلُوبٌ يَوْمَئِذٍ وَاجِفَةٌ ﴿٨﴾ أَبْصَٰرُهَا خَٰشِعَةٌ ﴿٩﴾
يَقُولُونَ أَءِنَّا لَمَرْدُودُونَ فِى ٱلْحَافِرَةِ ﴿١٠﴾ أَءِذَا كُنَّا عِظَٰمًا نَّخِرَةً ﴿١١﴾ قَالُوا۟
تِلْكَ إِذًا كَرَّةٌ خَاسِرَةٌ ﴿١٢﴾ فَإِنَّمَا هِىَ زَجْرَةٌ وَٰحِدَةٌ ﴿١٣﴾ فَإِذَا هُم بِٱلسَّاهِرَةِ
﴿١٤﴾ هَلْ أَتَىٰكَ حَدِيثُ مُوسَىٰٓ ﴿١٥﴾ إِذْ نَادَىٰهُ رَبُّهُۥ بِٱلْوَادِ ٱلْمُقَدَّسِ طُوًى ﴿١٦﴾


(31) Lalle masu taƙawa suna da babban rabo (32) (Su ne) gonaki da inabai (33) Da ‘yan mata tsaraiku (34) Da kofin (giya) cikakke (35) Ba sa jin maganar banza a cikinta ko kuma ƙarya (36) Sakamako ne daga Ubangijinka, kyauta ce a lissafe (gwargwadon aikin kowa)
(37) Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu (watau Allah) Mai rahama; (halittu) ba sa samun ikon yi masa magana daga gare Shi
(38) Ranar da Jibrilu da mala’iku za su tsaya sahu-sahu; (halittu) ba sa iya magana sai fa wanda (Allah) Mai rahama Ya yi wa izini, ya kuma faɗi abin da ya dace[1] (39) Wannan rana ce tabbatacciya; saboda haka wanda ya ga dama sai ya riƙi kyakkyawar makoma zuwa ga Ubangijinsa (40) Lalle Mun yi muku gargaɗin azaba ta kurkusa, a ranar da mutum zai ga abin da hannayensa suka gabatar (na alheri ko na sharri), kafiri kuma ya riƙa cewa: “Ina ma da na zama turɓaya[2]

Sura Nazi’at

(1) Na rantse da (mala’iku) masu cizgar (ran kafiri) mummunar cizga
(2) Da kuma (mala’iku) masu zare (ran mumini) sassauƙar zarewa
(3) Da kuma (mala’iku) masu ninƙaya (a sama don sauko da umarni) ninƙaya mai tsananin sauri (4) Sannan da (mala’iku) masu matuƙar rigegeniya (don zartar da umarnin Allah) (5) Sannan da (mala’iku) masu tsara al’amura (6) Ranar da mai girgizawa za ta yi girgiza (watau busar ƙaho ta farko) (7) Mai bin ta kuma za ta biyo ta (watau busa ta biyu) (8) Wasu zukata a wannan ranar a tsorace suke (9) Idanuwansu kuma a ƙasƙance suke (10) (A duniya) suna cewa: “Yanzu zai yiwu a dawo da mu a raye (bayan mutuwa)? (11) “Yanzu ko bayan mun zama ƙasusuwa rududdugaggu?” (12) Suka ce: “Idan ko ya yiwu, to wannan komawa ce mai cike da asara.” (13) To lalle ita kawai tsawa ce guda ɗaya tal! (14) Sai ga su a bayan ƙasa[2] (15) Shin labarin Musa ya zo maka? (16) Lokacin da Ubangijinsa Ya kirawo shi a kwari mai tsarki, (watau) Duwa?

(1) Watau kalmar tauhidi.

(2) Watau kowa da kowa ya fito da rai.


اذْهَبْ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ إِنَّهُ طَغَىٰ ﴿١٧﴾ فَقُلْ هَل لَّكَ إِلَىٰ أَن تَزَكَّىٰ ﴿١٨﴾ وَأَهْدِيَكَ
إِلَىٰ رَبِّكَ فَتَخْشَىٰ ﴿١٩﴾ فَأَرَاهُ الْآيَةَ الْكُبْرَىٰ ﴿٢٠﴾ فَكَذَّبَ وَعَصَىٰ ﴿٢١﴾ ثُمَّ
أَدْبَرَ يَسْعَىٰ ﴿٢٢﴾ فَحَشَرَ فَنَادَىٰ ﴿٢٣﴾ فَقَالَ أَنَا رَبُّكُمُ الْأَعْلَىٰ ﴿٢٤﴾ فَأَخَذَهُ
اللَّهُ نَكَالَ الْآخِرَةِ وَالْأُولَىٰ ﴿٢٥﴾ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبْرَةً لِّمَن يَخْشَىٰ ﴿٢٦﴾
ءَأَنتُمْ أَشَدُّ خَلْقًا أَمِ السَّمَاءُ بَنَاهَا ﴿٢٧﴾ رَفَعَ سَمْكَهَا فَسَوَّاهَا ﴿٢٨﴾
وَأَغْطَشَ لَيْلَهَا وَأَخْرَجَ ضُحَاهَا ﴿٢٩﴾ وَالْأَرْضَ بَعْدَ ذَٰلِكَ دَحَاهَا ﴿٣٠﴾
أَخْرَجَ مِنْهَا مَاءَهَا وَمَرْعَاهَا ﴿٣١﴾ وَالْجِبَالَ أَرْسَاهَا ﴿٣٢﴾ مَتَاعًا لَّكُمْ
وَلِأَنْعَامِكُمْ ﴿٣٣﴾ فَإِذَا جَاءَتِ الطَّامَّةُ الْكُبْرَىٰ ﴿٣٤﴾ يَوْمَ يَتَذَكَّرُ الْإِنسَانُ
مَا سَعَىٰ ﴿٣٥﴾ وَبُرِّزَتِ الْجَحِيمُ لِمَن يَرَىٰ ﴿٣٦﴾ فَأَمَّا مَن طَغَىٰ ﴿٣٧﴾ وَآثَرَ
الْحَيَاةَ الدُّنْيَا ﴿٣٨﴾ فَإِنَّ الْجَحِيمَ هِيَ الْمَأْوَىٰ ﴿٣٩﴾ وَأَمَّا مَنْ خَافَ
مَقَامَ رَبِّهِ وَنَهَى النَّفْسَ عَنِ الْهَوَىٰ ﴿٤٠﴾ فَإِنَّ الْجَنَّةَ هِيَ الْمَأْوَىٰ
﴿٤١﴾ يَسْأَلُونَكَ عَنِ السَّاعَةِ أَيَّانَ مُرْسَاهَا ﴿٤٢﴾ فِيمَ أَنتَ مِن
ذِكْرَاهَا ﴿٤٣﴾ إِلَىٰ رَبِّكَ مُنتَهَاهَا ﴿٤٤﴾ إِنَّمَا أَنتَ مُنذِرُ مَن يَخْشَاهَا
﴿٤٥﴾ كَأَنَّهُمْ يَوْمَ يَرَوْنَهَا لَمْ يَلْبَثُوا إِلَّا عَشِيَّةً أَوْ ضُحَاهَا ﴿٤٦﴾
سُورَةُ عَبَسَ

(17) (Aka ce da shi): Ka tafi zuwa ga Fir'auna, haƙiƙa shi ya yi ɗagawa
(18) Sai ka ce: "Shin zai yiwu gare ka kuwa ka tsarkaka?
(19) "In kuma shiryar da kai zuwa ga Ubangijinka, sai ka ji tsoron Sa?
(20) Sai ya nuna masa babbar aya[1]
(21) Sai ya ƙaryata ya kuma kangare
(22) Sannan ya ba da baya yana ta gaggawa
(23) Sai ya tattara (jama'arsa) sai ya yi shela
(24) Sai ya ce, "Ni ne ubangijinku mafi girma!"
(25)Saboda haka Allah Ya kama shi da azabar lahira (watau Jahannama) da ta duniya (watau nutse wa a ruwa) (26) Lalle a game da wannan tabbas akwai izina ga wanda yake tsoron (Allah) (27) Yanzu ku ne halittarku ta fi tsanani ko kuwa sama wadda Shi ne Ya gina ta? (28) Ya ɗaukaka rufinta Ya kuma daidaita ta[2] (29) Ya lulluɓe darenta da duhu Ya kuma fitar da hasken hantsinta (30) Kasa kuma bayan haka Ya shimfiɗa ta (31) Ya fitar da ruwanta da makiyayarta daga gare ta (32) Duwatsu kuma Ya kafa su (33) Don jin daɗinku da na dabbobinku (34) Sannan idan mafi girman busar ƙaho ta zo (watau busa ta biyu) (35) A ranar da mutum zai tuna abin da ya aikata (36) Aka kuma bayyana (wutar) Jahimu ga kowane mai gani (37) To (a wannan ranar) duk wanda ya yi ɗagawa (38) Ya kuma fifita rayuwar duniya (39) To lalle (wutar) Jahimu ita ce makoma (40) Duk wanda kuma ya ji tsoron tsayuwa gaban Ubangijinsa, ya kuma hana zuciya bin abin da take so (41) To lalle Aljanna ita ce makoma (42) Suna tambayar ka game da alƙiyama, yaushe ne lokacinta? (43) Me ya gama ka da ambaton lokacinta? (44) Zuwa ga Ubangijinka ne iyakacin saninta yake[3] (45) Kai dai kawai mai gargaɗin wanda yake tsoron ta ne (46) Kai ka ce su ranar da za su gan ta ba su zauna ba (a duniya) face wani yammaci ko kuma hantsinta

(1) Watau ya nuna masa hannun mai haske kamar fitila da kuma sandarsa mai rikixa ta zama macijiya.

(2) Watau ya zama babu wata varaka ko tsagewa ko wani aibi tare da ita.

(3) Watau Allah ne kaxai ya san lokacin aukuwarta.

Sura Abasa

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

عَبَسَ وَتَوَلَّىٰٓ ١ أَن جَآءَهُ ٱلْأَعْمَىٰ ٢ وَمَا يُدْرِيكَ لَعَلَّهُۥ يَزَّكَّىٰٓ ٣
أَوْ يَذَّكَّرُ فَتَنفَعَهُ ٱلذِّكْرَىٰٓ ٤ أَمَّا مَنِ ٱسْتَغْنَىٰ ٥ فَأَنتَ لَهُۥ تَصَدَّىٰ
٦ وَمَا عَلَيْكَ أَلَّا يَزَّكَّىٰ ٧ وَأَمَّا مَن جَآءَكَ يَسْعَىٰ ٨ وَهُوَ يَخْشَىٰ ٩
فَأَنتَ عَنْهُ تَلَهَّىٰ ١٠ كَلَّآ إِنَّهَا تَذْكِرَةٌ ١١ فَمَن شَآءَ ذَكَرَهُۥ ١٢ فِى صُحُفٍ
مُّكَرَّمَةٍ ١٣ مَّرْفُوعَةٍ مُّطَهَّرَةٍۭ ١٤ بِأَيْدِى سَفَرَةٍ ١٥ كِرَامٍۭ بَرَرَةٍ ١٦
قُتِلَ ٱلْإِنسَٰنُ مَآ أَكْفَرَهُۥ ١٧ مِنْ أَىِّ شَىْءٍ خَلَقَهُۥ ١٨ مِن نُّطْفَةٍ
خَلَقَهُۥ فَقَدَّرَهُۥ ١٩ ثُمَّ ٱلسَّبِيلَ يَسَّرَهُۥ ٢٠ ثُمَّ أَمَاتَهُۥ فَأَقْبَرَهُۥ ٢١ ثُمَّ إِذَا
شَآءَ أَنشَرَهُۥ ٢٢ كَلَّا لَمَّا يَقْضِ مَآ أَمَرَهُۥ ٢٣ فَلْيَنظُرِ ٱلْإِنسَٰنُ إِلَىٰ طَعَامِهِۦٓ
٢٤ أَنَّا صَبَبْنَا ٱلْمَآءَ صَبًّا ٢٥ ثُمَّ شَقَقْنَا ٱلْأَرْضَ شَقًّا ٢٦ فَأَنۢبَتْنَا فِيهَا
حَبًّا ٢٧ وَعِنَبًا وَقَضْبًا ٢٨ وَزَيْتُونًا وَنَخْلًا ٢٩ وَحَدَآئِقَ غُلْبًا ٣٠ وَفَٰكِهَةً
وَأَبًّا ٣١ مَّتَٰعًا لَّكُمْ وَلِأَنْعَٰمِكُمْ ٣٢ فَإِذَا جَآءَتِ ٱلصَّآخَّةُ ٣٣ يَوْمَ يَفِرُّ
ٱلْمَرْءُ مِنْ أَخِيهِ ٣٤ وَأُمِّهِۦ وَأَبِيهِ ٣٥ وَصَٰحِبَتِهِۦ وَبَنِيهِ ٣٦ لِكُلِّ
ٱمْرِئٍ مِّنْهُمْ يَوْمَئِذٍ شَأْنٌ يُغْنِيهِ ٣٧ وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ مُّسْفِرَةٌ
٣٨ ضَاحِكَةٌ مُّسْتَبْشِرَةٌ ٣٩ وَوُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ عَلَيْهَا غَبَرَةٌ ٤٠

(1) Ya ɗaure fuska[1], ya kuma ba da baya
(2) Don makaho[2] ya zo masa
(3) Me kuma zai sanar da kai cewa watakila shi ne zai tsarkaka?
(4) Ko ya wa'azantu, sai wa'azin ya amfane shi?
(5) Amma wanda ya wadatu (daga wa'azinka)
(6) To kai shi kake fuskanta
(7) Babu kuwa komai a kanka don ya ki ya tsarkaka
(8) Amma kuma wanda ya zo maka yana sauri
(9) Alhali kuma shi yana tsoron (Allah)
(10) To kai shi kake kawar wa da kai (11) Abin ba haka yake ba, lalle (wannan da'awar) wa'azi ne (12) Don haka wanda ya ga dama ya wa'azantu (13) (Wannan Alkur'ani) yana cikin takardu ababan girmamawa (14) Maɗaukaka, tsarkaka (15) A hannayen jakadu (mala'iku) (16) Manya masu biyayya (17) An la'anci mutum, me ya kai tsananin kafircinsa! (18) Shin daga wane abu ne (Allah) Ya halicce shi? (19) Daga maniyyi ne Ya halicce shi, sannan Ya ƙaddara shi (matakai a halitta) (20) Sannan tafarki (na rayuwa) Ya hore masa shi (21) Sannan Ya kashe shi, sai Ya sa shi cikin ƙabarinsa (22) Sannan in Ya ga dama Ya tashe shi (23) Fafau (zaton mutum) ba haka ne ba, har yanzu bai aikata abin da (Allah) Ya umarce shi ba (24) To mutum ya yi duba zuwa ga abincinsa mana? (25) Cewa lalle Mu Muka zubo da ruwan sama zubowa (26) Sannan Muka tsaga ƙasa tsagawa (27) Sai Muka tsiro da ƙwaya daga cikinta (28) Da inabai da ciyayi (29) Da zaitun da dabino (30) Da gonaki cike da itatuwa (31) Da kayan marmari da makiyaya (32) Don jin daɗinku da na dabbobinku (33) Sannan idan mai sa kurunta ta zo (watau busa ta farko) (34) A ranar da mutum yake guje wa ɗan'uwansa (35) Da uwarsa da ubansa (36) Da matarsa da 'ya'yansa (37) Kowane mutum daga cikinsu a wannan ranar yana da lamarin da ya sha kansa (38) Wasu fuskoki a wannan ranar masu haske ne (39) Masu dariya, masu farin ciki (40) Wasu fuskokin kuma a ranar akwai ƙura a kansu

(1) Shi ne Manzon Allah ( ).

(2) Shi ne Abdullahi xan Ummu Maktum, ya zo yana yi wa Annabi ( ) tambaya a lokacin shi kuma yana qoqarin janyo hankalin shugabannin Quraishawa zuwa ga Musulunci

تَرْهَقُهَا قَتَرَةٌ ﴿٤١﴾ أُولَٰئِكَ هُمُ الْكَفَرَةُ الْفَجَرَةُ ﴿٤٢﴾

سُورَةُ التَّكْوِيرِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

إِذَا الشَّمْسُ كُوِّرَتْ ﴿١﴾ وَإِذَا النُّجُومُ انكَدَرَتْ ﴿٢﴾ وَإِذَا الْجِبَالُ
سُيِّرَتْ ﴿٣﴾ وَإِذَا الْعِشَارُ عُطِّلَتْ ﴿٤﴾ وَإِذَا الْوُحُوشُ حُشِرَتْ
﴿٥﴾ وَإِذَا الْبِحَارُ سُجِّرَتْ ﴿٦﴾ وَإِذَا النُّفُوسُ زُوِّجَتْ ﴿٧﴾ وَإِذَا
الْمَوْءُودَةُ سُئِلَتْ ﴿٨﴾ بِأَيِّ ذَنبٍ قُتِلَتْ ﴿٩﴾ وَإِذَا الصُّحُفُ نُشِرَتْ
﴿١٠﴾ وَإِذَا السَّمَاءُ كُشِطَتْ ﴿١١﴾ وَإِذَا الْجَحِيمُ سُعِّرَتْ ﴿١٢﴾ وَإِذَا الْجَنَّةُ
أُزْلِفَتْ ﴿١٣﴾ عَلِمَتْ نَفْسٌ مَّا أَحْضَرَتْ ﴿١٤﴾ فَلَا أُقْسِمُ بِالْخُنَّسِ ﴿١٥﴾
الْجَوَارِ الْكُنَّسِ ﴿١٦﴾ وَاللَّيْلِ إِذَا عَسْعَسَ ﴿١٧﴾ وَالصُّبْحِ إِذَا تَنَفَّسَ ﴿١٨﴾
إِنَّهُ لَقَوْلُ رَسُولٍ كَرِيمٍ ﴿١٩﴾ ذِي قُوَّةٍ عِندَ ذِي الْعَرْشِ مَكِينٍ ﴿٢٠﴾ مُّطَاعٍ
ثَمَّ أَمِينٍ ﴿٢١﴾ وَمَا صَاحِبُكُم بِمَجْنُونٍ ﴿٢٢﴾ وَلَقَدْ رَآهُ بِالْأُفُقِ الْمُبِينِ
﴿٢٣﴾ وَمَا هُوَ عَلَى الْغَيْبِ بِضَنِينٍ ﴿٢٤﴾ وَمَا هُوَ بِقَوْلِ شَيْطَانٍ رَّجِيمٍ ﴿٢٥﴾
فَأَيْنَ تَذْهَبُونَ ﴿٢٦﴾ إِنْ هُوَ إِلَّا ذِكْرٌ لِّلْعَالَمِينَ ﴿٢٧﴾ لِمَن شَاءَ مِنكُمْ أَن
يَسْتَقِيمَ ﴿٢٨﴾ وَمَا تَشَاءُونَ إِلَّا أَن يَشَاءَ اللَّهُ رَبُّ الْعَالَمِينَ ﴿٢٩﴾

Sura Takwir

(1) Idan rana aka naɗe ta[1]
(2) Idan kuma taurari suka farfaɗo
(3) Idan kuma duwatsu aka tafiyar da su
(4) Idan kuma raƙuma masu ciki aka bar su ba makiyayi
(5) Idan kuma namun daji aka tattara su[2] (6) Idan kuma koguna aka rura su (suka zama wuta) (7) Idan kuma rayuka aka haɗa su (da jinsinsu)
(8) Idan kuma yarinyar da aka binne da rai aka tambaye ta (9) Da wane laifi ne aka kashe ta? (10) Idan kuma takardun (ayyuka) aka baza su[3] (11) Idan kuma sama aka ɗaye ta (12) Idan kuma wutar Jahimu aka hura ta (13) Idan kuma Aljanna aka kusanto da ita[4] (14) To kowane rai ya san abin da ya halarto (da shi na ayyuka) (15) To ina rantsuwa da taurari masu ɓuya[5] (16) Masu gudu zuwa masaukansu (17) Da kuma dare idan ya yi duhu (18) Da kuma asuba idan ta keto (19) Lalle shi (Alƙur'ani) magana ce ta Manzo mai karamci[6] (20) Ma'abocin ƙarfi a wurin Mai Al'arshi, kuma mai babban matsayi (21) Wanda ake yi wa biyayya ne a can (sama), amintacce (22) Mutumin naku kuma (watau Ma'aiki) ba mahaukaci ba ne (23) Haƙiƙa kuma ya gan shi a sararin sama mabayyani[7] (24) Shi kuma ba mai rowa ba ne game da wahayi (25) Kuma shi (Alƙur'ani) ba zancen Shaiɗan ne la'ananne ba (26) To ina za ku dosa ne[8]? (27) Shi ba wani abu ba ne sai wa'azi ga talikai (28) Ga wanda ya ga dama daga cikinku ya bi hanya madaidaiciya (29) Ku kuma ba za ku iya ganin dama ba sai Allah Ubangijin talikai Ya ga dama

(1) Watau aka haxa ta da wata wuri xaya, aka kuma tafiyar da haskenta.
(2) Watau aka tattara su wuri guda tare da 'yan'adam.
(3) Watau don kowa ya karanta takardarsa da kansa.
(4) Watau aka matso da ita dab da masu taqawa.
(5) Watau suna vuya lokacin hudowar hasken asuba, kamar yadda gada take voyewa a cikin gidanta.
(6) Watau Mala'ika Jibrilu ( ) wanda Allah ya amince masa ya isar wa da Manzon Allah ( ) zancensa.
(7) Watau Annabi ( ) ya ga Mala'ika Jibrilu ( ) a surarsa ta asali a sararin samaniya.
(8) Watau ina mushirikai suka dosa wajen qaryata Alqur'an bayan sun ji hujjoji masu qarfi?



Sura Infiɗar

(1) Idan sama ta tsattsage
(2) Idan kuma taurari suka farfaɗo suka tarwatse
(3) Idan kuma koguna aka harhaɗe su
(4) Idan kuma ƙaburbura aka fito da matattun da ke cikinsu
(5) Kowane rai ya san abin da ya gabatar da wanda ya jirkintar
(6) Ya kai mutum, me ya ruɗe ka ne game da Ubangijinka Mai karamci?
(7) Wanda Ya halicce ka Ya kuma daidaita ka Ya miƙar da kai[1]?

سُورَةُ الانفِطَارِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

إِذَا السَّمَاءُ انفَطَرَتْ ﴿١﴾ وَإِذَا الْكَوَاكِبُ انتَثَرَتْ ﴿٢﴾ وَإِذَا الْبِحَارُ
فُجِّرَتْ ﴿٣﴾ وَإِذَا الْقُبُورُ بُعْثِرَتْ ﴿٤﴾ عَلِمَتْ نَفْسٌ مَّا قَدَّمَتْ
وَأَخَّرَتْ ﴿٥﴾ يَا أَيُّهَا الْإِنسَانُ مَا غَرَّكَ بِرَبِّكَ الْكَرِيمِ ﴿٦﴾ الَّذِي
خَلَقَكَ فَسَوَّاكَ فَعَدَلَكَ ﴿٧﴾ فِي أَيِّ صُورَةٍ مَّا شَاءَ رَكَّبَكَ ﴿٨﴾
كَلَّا بَلْ تُكَذِّبُونَ بِالدِّينِ ﴿٩﴾ وَإِنَّ عَلَيْكُمْ لَحَافِظِينَ ﴿١٠﴾ كِرَامًا
كَاتِبِينَ ﴿١١﴾ يَعْلَمُونَ مَا تَفْعَلُونَ ﴿١٢﴾ إِنَّ الْأَبْرَارَ لَفِي نَعِيمٍ ﴿١٣﴾ وَإِنَّ
الْفُجَّارَ لَفِي جَحِيمٍ ﴿١٤﴾ يَصْلَوْنَهَا يَوْمَ الدِّينِ ﴿١٥﴾ وَمَا هُمْ عَنْهَا بِغَائِبِينَ
﴿١٦﴾ وَمَا أَدْرَاكَ مَا يَوْمُ الدِّينِ ﴿١٧﴾ ثُمَّ مَا أَدْرَاكَ مَا يَوْمُ الدِّينِ
﴿١٨﴾ يَوْمَ لَا تَمْلِكُ نَفْسٌ لِّنَفْسٍ شَيْئًا ۖ وَالْأَمْرُ يَوْمَئِذٍ لِّلَّهِ ﴿١٩﴾

سُورَةُ المُطَفِّفِينَ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

وَيْلٌ لِّلْمُطَفِّفِينَ ﴿١﴾ الَّذِينَ إِذَا اكْتَالُوا عَلَى النَّاسِ يَسْتَوْفُونَ ﴿٢﴾
وَإِذَا كَالُوهُمْ أَو وَّزَنُوهُمْ يُخْسِرُونَ ﴿٣﴾ أَلَا يَظُنُّ أُولَٰئِكَ أَنَّهُم مَّبْعُوثُونَ ﴿٤﴾


(8) Ya harhaɗa ka cikin irin surar da Ya ga dama?
(9) A'a dai, kawai dai kuna ƙaryata ranar sakamako ne
(10) Kuma lalle akwai masu kula da ku[2]
(11) Masu daraja marubuta
(12) Suna sane da abin da kuke aikatawa
(13) Lalle mutanen kirki tabbas suna cikin ni'ima
(14) Lalle kuma fajirai tabbas suna cikin (wutar) Jahima
(15) Za su ƙonu da ita ranar sakamako
(16) Kuma su ba masu rabuwa ne da ita ba
(17) Kuma kai me ya sanar da kai mece ce ranar sakamako?
(18) Sannan me ya sanar da kai mece ce ranar sakamako?
(19) (Ita ce) ranar da wani rai ba ya mallakar wani amfani ga wani rai; al'amari kuwa (gaba ɗayansa) a wannan ranar yana ga Allah

Sura Muɗaffifin

(1) Tsananin azaba ya tabbata ga masu tauye ma'auni
(2) Waɗanda idan suka auna daga wajen mutane suna cikawa fal
(3) Idan kuwa su za su aunar, da mudu ne ko da sikeli, to sai su tauye
(4) Yanzu waɗannan ba sa zaton cewa su lalle za a tashe su?

(1) Watau ya lura da girman ni'imar da ya yi masa yayin da bai yi masa irin halittar jaki ba ko ta biri ko ta kare.

(2) Watau mala'iku.


لِيَوْمٍ عَظِيمٍ ۝٥ يَوْمَ يَقُومُ ٱلنَّاسُ لِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ۝٦ كَلَّآ إِنَّ كِتَٰبَ
ٱلْفُجَّارِ لَفِى سِجِّينٍ ۝٧ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا سِجِّينٌ ۝٨ كِتَٰبٌ مَّرْقُومٌ ۝٩
وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ۝١٠ ٱلَّذِينَ يُكَذِّبُونَ بِيَوْمِ ٱلدِّينِ ۝١١ وَمَا يُكَذِّبُ
بِهِۦٓ إِلَّا كُلُّ مُعْتَدٍ أَثِيمٍ ۝١٢ إِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِ ءَايَٰتُنَا قَالَ أَسَٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ
۝١٣ كَلَّا ۖ بَلْ ۜ رَانَ عَلَىٰ قُلُوبِهِم مَّا كَانُوا۟ يَكْسِبُونَ ۝١٤ كَلَّآ إِنَّهُمْ عَن رَّبِّهِمْ
يَوْمَئِذٍ لَّمَحْجُوبُونَ ۝١٥ ثُمَّ إِنَّهُمْ لَصَالُوا۟ ٱلْجَحِيمِ ۝١٦ ثُمَّ يُقَالُ هَٰذَا
ٱلَّذِى كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ۝١٧ كَلَّآ إِنَّ كِتَٰبَ ٱلْأَبْرَارِ لَفِى عِلِّيِّينَ ۝١٨
وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا عِلِّيُّونَ ۝١٩ كِتَٰبٌ مَّرْقُومٌ ۝٢٠ يَشْهَدُهُ ٱلْمُقَرَّبُونَ ۝٢١
إِنَّ ٱلْأَبْرَارَ لَفِى نَعِيمٍ ۝٢٢ عَلَى ٱلْأَرَآئِكِ يَنظُرُونَ ۝٢٣ تَعْرِفُ فِى
وُجُوهِهِمْ نَضْرَةَ ٱلنَّعِيمِ ۝٢٤ يُسْقَوْنَ مِن رَّحِيقٍ مَّخْتُومٍ ۝٢٥ خِتَٰمُهُۥ
مِسْكٌ ۚ وَفِى ذَٰلِكَ فَلْيَتَنَافَسِ ٱلْمُتَنَٰفِسُونَ ۝٢٦ وَمِزَاجُهُۥ مِن
تَسْنِيمٍ ۝٢٧ عَيْنًا يَشْرَبُ بِهَا ٱلْمُقَرَّبُونَ ۝٢٨ إِنَّ ٱلَّذِينَ أَجْرَمُوا۟ كَانُوا۟
مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ يَضْحَكُونَ ۝٢٩ وَإِذَا مَرُّوا۟ بِهِمْ يَتَغَامَزُونَ ۝٣٠
وَإِذَا ٱنقَلَبُوٓا۟ إِلَىٰٓ أَهْلِهِمُ ٱنقَلَبُوا۟ فَكِهِينَ ۝٣١ وَإِذَا رَأَوْهُمْ قَالُوٓا۟
إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ لَضَآلُّونَ ۝٣٢ وَمَآ أُرْسِلُوا۟ عَلَيْهِمْ حَٰفِظِينَ ۝٣٣

(5) A wata rana mai girma?
(6) Ranar da mutane za su tsaya gaban Ubangijin talikai?
(7) Tabbas, lalle littafin fajirai yana cikin Sijjinu
(8) Me kuma ya sanar da kai me ake ce wa Sijjinu?
(9) Littafi ne rubutacce[1]
(10) Tsananin azaba a wannan ranar ya tabbata ga masu ƙaryatawa
(11) Waɗanda suke ƙaryata ranar sakamako
(12) Babu kuwa mai ƙaryata ta sai duk wani mai shisshigi mai yawan saɓo
(13) Idan ana karanta masa ayoyinmu sai ya ce: "Wannan tatsuniyoyi ne na mutanen farko."
(14)A'a, abin ai ba haka ba ne; abin da suke aikatawa ne ya yi tsatsa a zukatansu (15) Tabbas! Lalle su haƙiƙa ababan kangewa ne daga (ganin) Ubangijinsu[2] a wannan rana (16) Sannan kuma lalle su tabbas masu shiga wutar Jahimu ne (17) Sannan za a ce: "Wannan ne abin da kuka kasance kuna ƙaryata shi." (18) Tabbas! Lalle littafin mutanen kirki haƙiƙa yana cikin Illiyyuna (19) Me ya sanar da kai mene ne Iliyyuna? (20) Wani littafi ne rubutacce[3] (21) (Mala'iku) makusanta suke halartar sa (22) Lalle masu biyayya tabbas suna cikin ni'ima (23) A kan gadaje suna kallo (24) Za ka gane hasken ni'ima a fuskokinsu[4] (25) Ana shayar da su giyar da aka rufe (bakin mazubinta) (26) (Har) ƙarshensa (ƙamshin) almiski ne. To game da wannan kuwa lalle masu gasa su yi gasa (27) Mahaɗinsa kuma daga ruwan tasnimu yake (28) Wani idon ruwa wanda bayi makusanta ne suke sha daga gare shi (29) Lalle waɗanda suka yi manyan laifuka[5] sun kasance suna yi wa waɗanda suka yi imani dariya (a duniya) (30) Kuma idan suka wuce ta wajensu sai su ƙiƙa zunɗen su (31) Idan kuma sun koma wurin iyalinsu sai su komo suna masu farin ciki[6] (32) Kuma idan sun gan su sai su ce: "Lalle waɗannan ɓatattu ne." (33) Ba a kuwa aiko su don su zama masu tsaron su ba

(1) Watau wanda ya qunshi cikakkun ayyukan fajirai cif-cif ba daxi babu ragi.
(2) Watau kafirai ba za su ga Allah ba a ranar alqiyama, kamar yadda suka kasa ganin gaskiya a nan duniya.
(3) Watau wanda aka tanada domin rubuta kyawawan ayyukan muminai cif-cif.
(4) Watau fuskokinsu suna sheqi da annuri.
(5) Watau kafirai.
(6) Watau saboda izgili da dariya da suka yi wa muminai.

فَٱلْيَوْمَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مِنَ ٱلْكُفَّارِ يَضْحَكُونَ ﴿٣٤﴾ عَلَى
ٱلْأَرَآئِكِ يَنظُرُونَ ﴿٣٥﴾ هَلْ ثُوِّبَ ٱلْكُفَّارُ مَا كَانُوا۟ يَفْعَلُونَ ﴿٣٦﴾

سُورَةُ الانشِقَاقِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِذَا ٱلسَّمَآءُ ٱنشَقَّتْ ﴿١﴾ وَأَذِنَتْ لِرَبِّهَا وَحُقَّتْ ﴿٢﴾ وَإِذَا ٱلْأَرْضُ مُدَّتْ
﴿٣﴾ وَأَلْقَتْ مَا فِيهَا وَتَخَلَّتْ ﴿٤﴾ وَأَذِنَتْ لِرَبِّهَا وَحُقَّتْ ﴿٥﴾ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلْإِنسَٰنُ إِنَّكَ كَادِحٌ إِلَىٰ رَبِّكَ كَدْحًا فَمُلَٰقِيهِ ﴿٦﴾ فَأَمَّا مَنْ أُوتِىَ
كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ ﴿٧﴾ فَسَوْفَ يُحَاسَبُ حِسَابًا يَسِيرًا ﴿٨﴾ وَيَنقَلِبُ
إِلَىٰٓ أَهْلِهِۦ مَسْرُورًا ﴿٩﴾ وَأَمَّا مَنْ أُوتِىَ كِتَٰبَهُۥ وَرَآءَ ظَهْرِهِۦ ﴿١٠﴾ فَسَوْفَ
يَدْعُوا۟ ثُبُورًا ﴿١١﴾ وَيَصْلَىٰ سَعِيرًا ﴿١٢﴾ إِنَّهُۥ كَانَ فِىٓ أَهْلِهِۦ مَسْرُورًا ﴿١٣﴾
إِنَّهُۥ ظَنَّ أَن لَّن يَحُورَ ﴿١٤﴾ بَلَىٰٓ ۚ إِنَّ رَبَّهُۥ كَانَ بِهِۦ بَصِيرًا ﴿١٥﴾ فَلَآ أُقْسِمُ
بِٱلشَّفَقِ ﴿١٦﴾ وَٱلَّيْلِ وَمَا وَسَقَ ﴿١٧﴾ وَٱلْقَمَرِ إِذَا ٱتَّسَقَ ﴿١٨﴾
لَتَرْكَبُنَّ طَبَقًا عَن طَبَقٍ ﴿١٩﴾ فَمَا لَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿٢٠﴾ وَإِذَا قُرِئَ
عَلَيْهِمُ ٱلْقُرْءَانُ لَا يَسْجُدُونَ ۩ ﴿٢١﴾ بَلِ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ يُكَذِّبُونَ
﴿٢٢﴾ وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا يُوعُونَ ﴿٢٣﴾ فَبَشِّرْهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿٢٤﴾

(34) To a wannan rana ne[1] waɗanda suka yi imani za su yi wa kafirai dariya
(35) Daga kan gadaje suna kallo
(36) Shin an saka wa kafirai abin da suka kasance suna aikatawa?

Sura Inshikak

(1) Idan sama ta tsattsage[2]
(2) Ta kuma saurari Ubangijinta, kuma ya wajaba (ta saurara)
(3) Kuma idan ƙasa aka miƙe ta
(4) Ta kuma jefar da abin da yake cikinta ta wofinta[3]
(5) Ta kuma saurari Ubangijinta kuma ya wajaba (ta saurara)
(6) Ya kai mutum, lalle kai mai yin aiki ne tuƙuru zuwa ga Ubangijinka, to mai haɗuwa da Shi ne
(7) To amma duk wanda aka bai wa littafinsa a hannunsa na dama
(8) To za a yi masa hisabi mai sauƙi[4]
(9) Ya kuma juyo zuwa ga iyalinsa yana farin ciki
(10) Amma wanda kuwa aka bai wa littafinsa ta bayan bayansa
(11) To zai yi kiran halaka
(12) Zai kuma shiga (wutar) Sa'ira
(13) Lalle a da shi ya kasance mai farin ciki ne cikin iyalinsa
(14) Lalle ya yi zaton ba zai koma (ga Allah) ba
(15) Haka yake, (zai koma), lalle Ubangijinsa Ya kasance Mai ganin sa ne
(16) To ina rantsuwa da shafaƙi
(17) Da kuma dare da abin da ya tattara
(18) Da kuma wata idan ya cika
(19) Tabbas za ku hau wani mataki bayan wani mataki[5]
(20) To me ya same su ne ba sa yin imani?
(21) Idan kuma an karanta musu Alƙur'ani ba sa yin sujjada?
(22) A'a, su dai waɗanda suka kafirce suna ƙaryatawa ne
(23) Allah kuwa (Shi) Ya fi sanin abin da suke ɓoyewa (a zukatansu)
(24) To ka yi musu albishir da azaba mai raɗaɗi

(1) Watau ranar alqiyama.
(2) Watau mala'iku suka yi ta saukowa.
(3) Watau cikinta ya koma fayau babu sauran wani abu.
(4) Watau ta hanyar bijiro ayyukansa a dunqule ba tare da binciken qwaqwaf ba.
(5) Watau na halittarsu, sai sun kasance xigon maniyyi, sannan su zama gudan jini sai kuma gudar tsoka, har zuwa cikar halittarsu.



إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمۡ أَجۡرٌ غَيۡرُ مَمۡنُونٖ ٢٥

سُورَةُ البُرُوجِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلسَّمَآءِ ذَاتِ ٱلۡبُرُوجِ ١ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡمَوۡعُودِ ٢ وَشَاهِدٖ وَمَشۡهُودٖ
٣ قُتِلَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡأُخۡدُودِ ٤ ٱلنَّارِ ذَاتِ ٱلۡوَقُودِ ٥ إِذۡ هُمۡ عَلَيۡهَا
قُعُودٞ ٦ وَهُمۡ عَلَىٰ مَا يَفۡعَلُونَ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ شُهُودٞ ٧ وَمَا نَقَمُواْ
مِنۡهُمۡ إِلَّآ أَن يُؤۡمِنُواْ بِٱللَّهِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَمِيدِ ٨ ٱلَّذِي لَهُۥ مُلۡكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدٌ ٩ إِنَّ ٱلَّذِينَ
فَتَنُواْ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ ثُمَّ لَمۡ يَتُوبُواْ فَلَهُمۡ عَذَابُ جَهَنَّمَ وَلَهُمۡ
عَذَابُ ٱلۡحَرِيقِ ١٠ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمۡ
جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡكَبِيرُ ١١ إِنَّ بَطۡشَ
رَبِّكَ لَشَدِيدٌ ١٢ إِنَّهُۥ هُوَ يُبۡدِئُ وَيُعِيدُ ١٣ وَهُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلۡوَدُودُ ١٤
ذُو ٱلۡعَرۡشِ ٱلۡمَجِيدُ ١٥ فَعَّالٞ لِّمَا يُرِيدُ ١٦ هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ٱلۡجُنُودِ
١٧ فِرۡعَوۡنَ وَثَمُودَ ١٨ بَلِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فِي تَكۡذِيبٖ ١٩ وَٱللَّهُ مِن
وَرَآئِهِم مُّحِيطُۢ ٢٠ بَلۡ هُوَ قُرۡءَانٞ مَّجِيدٞ ٢١ فِي لَوۡحٖ مَّحۡفُوظِۭ ٢٢

Sura Buruj

(1) Na rantse da sama ma'abociyar manziloli(1)
(2) Da ranar da aka yi alƙawarin zuwanta(2)
(3) Da mai shaida(3) da kuma abin yi wa shaida
(4) An la'anci ma'abota rami (na azabtar da muminai)(4)
(5) Na wuta mai ruruwa
(6) Yayin da suke zaune a gefentaa,
(7) Alhali su suna kallon abin da suke aikata wa muminai
(8) Babu kuwa abin da suke tuhumar su da shi sai don kawai sun yi imani da Allah Mabuwayi, Sha-yabo
(9) Wanda Yake da mulkin sammai da ƙasa. Allah kuma Mai ganin komai ne
(10) Lalle waɗanda suka azabtar da muminai maza da muminai mata sannan ba su tuba ba, to suna da azabar Jahannama, suna kuma da azabar ƙuna
(11) Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari suna da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Wannan kuwa shi ne babban rabo
(12) Lalle damƙar Ubangijinka tabbas mai tsanani ce
(13) Lalle Shi ne Yake farar (da komai) Yake kuma dawo (da shi)
(14) Shi ne kuma Mai gafara, Mai ƙaunar (bayinsa na ƙwarai)
(15) Ma'abocin Al'arshi Mai girma
(16) Mai aikata abin da Yake nufi
(17) Shin labarin rundunoni ya zo maka?
(18) (Su ne) Fir'auna da Samudawa
(19) A'a, su dai waɗanda suka kafirta suna cikin ƙaryatawa ne
(20) Allah kuwa Yana kewaye da su (da iliminsa)
(21) A'a, shi dai Alƙur'ani ne mai girma
(22) A cikin Lauhul-Mahafuzu

(1) Watau manziloli na rana da wata da taurari.
(2) Watau ranar alqiyama.
(3) Watau kamar Annabi da zai ba da shaida game da al'ummarsa.
(4) Wani azzalumin sarki ne da aka yi a Najrana ta qasar Yaman kafin aiko Annabi ( ) wanda aka haqa masa rami aka hura wuta, ya riqa jefa muminai a cikinsa yana qona su da ransu.

Sura Darik

(1) Na rantse da sama da (tauraro) mai zuwa cikin dare
(2) Me ya sanar da kai mai zuwa cikin dare?
(3) Tauraro ne mai keta (duhu) da haskensa
(4) Ba wani rai face akwai mai tsaron sa
(5) To mutum ya duba mana, daga me aka halicce shi?
(6) An halicce shi ne daga wani ruwa mai ingizar juna[1]
(7) Mai fita daga tsakanin tsatso da karankarma[2]
(8) Lalle Shi (Allah) Mai iko ne a kan dawo da shi
(9) A ranar da za a bayyana asirai[3]

سُورَةُ الطَّارِقِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

وَالسَّمَاءِ وَالطَّارِقِ ﴿١﴾ وَمَا أَدْرَاكَ مَا الطَّارِقُ ﴿٢﴾ النَّجْمُ الثَّاقِبُ
﴿٣﴾ إِن كُلُّ نَفْسٍ لَّمَّا عَلَيْهَا حَافِظٌ ﴿٤﴾ فَلْيَنظُرِ الْإِنسَانُ مِمَّ خُلِقَ ﴿٥﴾
خُلِقَ مِن مَّاءٍ دَافِقٍ ﴿٦﴾ يَخْرُجُ مِن بَيْنِ الصُّلْبِ وَالتَّرَائِبِ ﴿٧﴾ إِنَّهُ عَلَىٰ
رَجْعِهِ لَقَادِرٌ ﴿٨﴾ يَوْمَ تُبْلَى السَّرَائِرُ ﴿٩﴾ فَمَا لَهُ مِن قُوَّةٍ وَلَا نَاصِرٍ
﴿١٠﴾ وَالسَّمَاءِ ذَاتِ الرَّجْعِ ﴿١١﴾ وَالْأَرْضِ ذَاتِ الصَّدْعِ ﴿١٢﴾ إِنَّهُ
لَقَوْلٌ فَصْلٌ ﴿١٣﴾ وَمَا هُوَ بِالْهَزْلِ ﴿١٤﴾ إِنَّهُمْ يَكِيدُونَ كَيْدًا ﴿١٥﴾
وَأَكِيدُ كَيْدًا ﴿١٦﴾ فَمَهِّلِ الْكَافِرِينَ أَمْهِلْهُمْ رُوَيْدًا ﴿١٧﴾

سُورَةُ الأَعْلَى

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

سَبِّحِ اسْمَ رَبِّكَ الْأَعْلَى ﴿١﴾ الَّذِي خَلَقَ فَسَوَّىٰ ﴿٢﴾ وَالَّذِي قَدَّرَ فَهَدَىٰ
﴿٣﴾ وَالَّذِي أَخْرَجَ الْمَرْعَىٰ ﴿٤﴾ فَجَعَلَهُ غُثَاءً أَحْوَىٰ ﴿٥﴾ سَنُقْرِئُكَ
فَلَا تَنسَىٰ ﴿٦﴾ إِلَّا مَا شَاءَ اللَّهُ إِنَّهُ يَعْلَمُ الْجَهْرَ وَمَا يَخْفَىٰ ﴿٧﴾ وَنُيَسِّرُكَ
لِلْيُسْرَىٰ ﴿٨﴾ فَذَكِّرْ إِن نَّفَعَتِ الذِّكْرَىٰ ﴿٩﴾ سَيَذَّكَّرُ مَن يَخْشَىٰ ﴿١٠﴾

(10) To ba shi da wani ƙarfi ko wani mataimaki
(11) Na rantse da sama ma'abociyar dawo (da ruwa)
(12) Da kuma ƙasa ma'abociyar tsagewa (shuka ta fito)
(13) Lalle shi (Alƙur'ani) magana ce mai tsage gaskiya
(14) Kuma shi ba zancen banza ba ne
(15) Lalle su (kafirai) suna ƙulla mummunan makirci
(16) Ni kuma ina shirya musu mummunan sakamako
(17) To sai ka saurara wa kafirai, ka saurara musu kaɗan

Sura A'ala

(1) Ka tsarkake sunan Ubangijinka Mafi ɗaukaka
(2) Wanda Ya yi halitta sai Ya daidaita (ta)
(3) Wanda kuma Ya ƙaddara (abubuwa) sannan Ya shiryar (da halittarsa)
(4) Wanda kuma Ya fitar da makiyaya
(5) Sai Ya mayar da ita duddugaggiya mai baƙi
(6) Za Mu karantar da kai (Alƙur'ani) don haka ba za ka manta ba
(7) Sai abin da Allah Ya ga dama, Lalle Shi Yana sane da bayyanannen (abu) da kuma abin da yake ɓuya
(8) Kuma za Mu sauƙaƙe maka (al'umara) mafiya sauƙi[4]
(9) To ka yi wa'azi idan wa'azin zai yi amfani
(10) Wanda yake tsoron Allah zai wa'azantu

(1) Watau maniyyi.
(2) Watau daga tsakanin qashin bayan namiji da qasusuwan qirjinsa.
(3) Watau abubuwan da suke cikin zukata na niyyoyi da aqidu da sauransu.
(4) Watau al'ummuransa na addini da na rayuwa, domin ya sa damar da saqon Allah a cikin nutsuwa.

وَيَتَجَنَّبُهَا ٱلْأَشْقَى ﴿١١﴾ ٱلَّذِى يَصْلَى ٱلنَّارَ ٱلْكُبْرَىٰ ﴿١٢﴾ ثُمَّ لَا يَمُوتُ
فِيهَا وَلَا يَحْيَىٰ ﴿١٣﴾ قَدْ أَفْلَحَ مَن تَزَكَّىٰ ﴿١٤﴾ وَذَكَرَ ٱسْمَ رَبِّهِۦ فَصَلَّىٰ ﴿١٥﴾
بَلْ تُؤْثِرُونَ ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا ﴿١٦﴾ وَٱلْءَاخِرَةُ خَيْرٌ وَأَبْقَىٰٓ ﴿١٧﴾ إِنَّ
هَٰذَا لَفِى ٱلصُّحُفِ ٱلْأُولَىٰ ﴿١٨﴾ صُحُفِ إِبْرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ ﴿١٩﴾

سُورَةُ الغَاشِيَة

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

هَلْ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ٱلْغَٰشِيَةِ ﴿١﴾ وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ خَٰشِعَةٌ ﴿٢﴾ عَامِلَةٌ
نَّاصِبَةٌ ﴿٣﴾ تَصْلَىٰ نَارًا حَامِيَةً ﴿٤﴾ تُسْقَىٰ مِنْ عَيْنٍ ءَانِيَةٍ ﴿٥﴾ لَّيْسَ
لَهُمْ طَعَامٌ إِلَّا مِن ضَرِيعٍ ﴿٦﴾ لَّا يُسْمِنُ وَلَا يُغْنِى مِن جُوعٍ ﴿٧﴾ وُجُوهٌ
يَوْمَئِذٍ نَّاعِمَةٌ ﴿٨﴾ لِّسَعْيِهَا رَاضِيَةٌ ﴿٩﴾ فِى جَنَّةٍ عَالِيَةٍ ﴿١٠﴾ لَّا تَسْمَعُ
فِيهَا لَٰغِيَةً ﴿١١﴾ فِيهَا عَيْنٌ جَارِيَةٌ ﴿١٢﴾ فِيهَا سُرُرٌ مَّرْفُوعَةٌ ﴿١٣﴾ وَأَكْوَابٌ
مَّوْضُوعَةٌ ﴿١٤﴾ وَنَمَارِقُ مَصْفُوفَةٌ ﴿١٥﴾ وَزَرَابِىُّ مَبْثُوثَةٌ ﴿١٦﴾ أَفَلَا يَنظُرُونَ
إِلَى ٱلْإِبِلِ كَيْفَ خُلِقَتْ ﴿١٧﴾ وَإِلَى ٱلسَّمَآءِ كَيْفَ رُفِعَتْ ﴿١٨﴾ وَإِلَى
ٱلْجِبَالِ كَيْفَ نُصِبَتْ ﴿١٩﴾ وَإِلَى ٱلْأَرْضِ كَيْفَ سُطِحَتْ ﴿٢٠﴾
فَذَكِّرْ إِنَّمَآ أَنتَ مُذَكِّرٌ ﴿٢١﴾ لَّسْتَ عَلَيْهِم بِمُصَيْطِرٍ ﴿٢٢﴾

(11) Mafi shaqiyanci[1] kuma zai nesance shi
(12) Wanda zai shiga wuta mafi girma
(13) Sannan ba zai mutu a cikinta ba kuma ba zai rayu (rayuwa mai daxi) ba
(14) Haqiqa wanda ya tsarkaka ya rabauta
(15) Ya kuma ambaci sunan Ubangijinsa sannan ya yi salla
(16) Ba haka ba, ku dai kuna fifita rayuwar duniya ne
(17) Lahira kuwa ita ta fi alheri ta kuma fi wanzuwa
(18) Lalle wannan (batu) tabbas yana cikin littattafan farko
(19) Littattafan Ibrahimu da Musa

Sura Ghashiya

(1) Shin labarin mai lullubewa da (tsoro) ya zo maka?
(2) Wasu fuskoki a wannan ranar ƙasƙantattu ne
(3) Masu aiki ne (tuƙuru)[2] masu shan wahala
(4) Za su shiga wuta mai tsananin ƙuna
(5) Za a shayar da su daga idon ruwa mai tsananin zafi
(6) Ba su da wani abinci sai na ƙayar tsidau
(7) Ba ya sa ƙiba kuma ba ya maganin yunwa
(8) Waɗansu fuskokin kuwa a wannan ranar ni'imtattu ne
(9) Masu gamsuwa ne da (sakamakon) ayyukansu
(10) (Suna) cikin Aljanna maɗaukakiya[3]
(11) Ba a jin zancen banza a cikinta
(12) A cikinta akwai marmaro mai gudana
(13) A cikinta akwai gadaje maɗaukaka,
(14) Da kofuna a ajijjiye
(15) Da matasan kai a jejjere
(16) Da dardumai a shisshimfiɗe
(17) Shin ba sa duban raƙumi yadda aka halicce shi?
(18) Da kuma sama yadda aka ɗaga ta?
(19) Da kuma duwatsu yadda aka kakkafa su?
(20) Da kuma ƙasa yadda aka shimfiɗa ta?
(21) To ka yi wa'azi, lalle kai mai wa'azi ne kawai
(22) Kai ba mai tilasta su ba ne

(1) Watau kafiri tavavve.
(2) Watau a wutar Jahannama.
(3) Watau xaukaka ta daraja da xaukaka ta muhalli, domin gidajen Aljanna benaye ne wasu kan wasu.

إِلَّا مَن تَوَلَّىٰ وَكَفَرَ ﴿٢٣﴾ فَيُعَذِّبُهُ ٱللَّهُ ٱلْعَذَابَ ٱلْأَكْبَرَ ﴿٢٤﴾
إِنَّ إِلَيْنَآ إِيَابَهُمْ ﴿٢٥﴾ ثُمَّ إِنَّ عَلَيْنَا حِسَابَهُم ﴿٢٦﴾

سُورَةُ الْفَجْرِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلْفَجْرِ ﴿١﴾ وَلَيَالٍ عَشْرٍ ﴿٢﴾ وَٱلشَّفْعِ وَٱلْوَتْرِ ﴿٣﴾ وَٱلَّيْلِ إِذَا يَسْرِ ﴿٤﴾
هَلْ فِي ذَٰلِكَ قَسَمٌ لِّذِي حِجْرٍ ﴿٥﴾ أَلَمْ تَرَ كَيْفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِعَادٍ ﴿٦﴾
إِرَمَ ذَاتِ ٱلْعِمَادِ ﴿٧﴾ ٱلَّتِي لَمْ يُخْلَقْ مِثْلُهَا فِي ٱلْبِلَادِ ﴿٨﴾ وَثَمُودَ ٱلَّذِينَ
جَابُوا۟ ٱلصَّخْرَ بِٱلْوَادِ ﴿٩﴾ وَفِرْعَوْنَ ذِي ٱلْأَوْتَادِ ﴿١٠﴾ ٱلَّذِينَ طَغَوْا۟ فِي
ٱلْبِلَادِ ﴿١١﴾ فَأَكْثَرُوا۟ فِيهَا ٱلْفَسَادَ ﴿١٢﴾ فَصَبَّ عَلَيْهِمْ رَبُّكَ سَوْطَ
عَذَابٍ ﴿١٣﴾ إِنَّ رَبَّكَ لَبِٱلْمِرْصَادِ ﴿١٤﴾ فَأَمَّا ٱلْإِنسَٰنُ إِذَا مَا ٱبْتَلَىٰهُ
رَبُّهُۥ فَأَكْرَمَهُۥ وَنَعَّمَهُۥ فَيَقُولُ رَبِّيٓ أَكْرَمَنِ ﴿١٥﴾ وَأَمَّآ إِذَا مَا ٱبْتَلَىٰهُ
فَقَدَرَ عَلَيْهِ رِزْقَهُۥ فَيَقُولُ رَبِّيٓ أَهَٰنَنِ ﴿١٦﴾ كَلَّا ۖ بَل لَّا تُكْرِمُونَ
ٱلْيَتِيمَ ﴿١٧﴾ وَلَا تَحَٰٓضُّونَ عَلَىٰ طَعَامِ ٱلْمِسْكِينِ ﴿١٨﴾ وَتَأْكُلُونَ
ٱلتُّرَاثَ أَكْلًا لَّمًّا ﴿١٩﴾ وَتُحِبُّونَ ٱلْمَالَ حُبًّا جَمًّا ﴿٢٠﴾ كَلَّآ ۖ إِذَا
دُكَّتِ ٱلْأَرْضُ دَكًّا دَكًّا ﴿٢١﴾ وَجَآءَ رَبُّكَ وَٱلْمَلَكُ صَفًّا صَفًّا ﴿٢٢﴾

(23) Sai dai wanda ya ba da baya ya kuma kafirce
(24) To Allah zai azabtar da shi azaba mafi girma[1]
(25) Lalle zuwa gare Mu ne makomarsu take
(26) Sannan kuma a kanmu ne hisabinsu yake

Sura Fajr

(1) Na rantse da alfijir
(2) Da kuma darare goma[2]
(3) Da kuma abin da yake cika[3] da kuma mara[4]
(4) Da kuma dare lokacin da yake tafiya (cikin duhu)
(5) Shin a game da waɗannan akwai rantsuwa (mai gamsarwa) ga mai hankali[5]? (6) Shin ba ka ga yadda Ubangijinka Ya aikata ba ga Adawa? (7) (Watau ƙabilar) Iramu ma'abociyar tsawo (8) Wadda ba a halicci irinta ba a cikin garuruwa (a tsananin ƙarfi) (9) Da kuma Samudawa waɗanda suka fafe duwatsu a wurin da ake kira Wadil-Kura (10) Da kuma Fir'auna ma'abocin turaku (11) Waɗanda suka yi ɗagawa a cikin garuruwa (12) Suka kuma yawaita ɓarna a cikinsu (13) Sai Ubangijinka Ya saukar musu azaba mai tsanani (14) Lalle Ubangijinka tabbas Yana nan a madakata[6] (15) Amma kuma mutum idan Ubangijinsa Ya jarrabe shi sai Ya karrama shi, Ya kuma yi masa ni'ima, sai ya ce: "Ubangijina Ya karrama ni." (16) Amma kuma idan Ya jarrabe shi sai Ya ƙuntata masa a arzikinsa, sai ya ce: "Ubangijina Ya wulaƙanta ni." (17) Faufau, ba haka ba ne; ku ba kwa karrama maraya ne (18) Kuma ba kwa kwaɗaitar da juna kan ciyar da miskinai (19) Kuma kuna cinye dukiyar gadon marayu mummunan ci (20) Kuma kuna son dukiya so mai yawa (21) Ba haka ne ba, idan aka girgiza ƙasa matuƙar girgiza (22) Ubangijinka kuma Ya zo[7] tare da mala'iku sahu-sahu

(1) Watau wutar Jahannama inda zai dawwama a cikinta har abada.
(2) Watau kwanaki goma na farkon watan Zulhijja.
(3) Watau bibbiyu ko hurhuxu ko shida-shida da sauransu.
(4) Watau xaya ko uku ko biyar da sauransu.
(5) Watau duk mai hankali zai gamsu da waxannan rantse-rantse.
(6) Watau yana wurin da yake hangen xaukacin ayyukan bayinsa.
(7) Watau don yin hukunci a tsakanin bayinsa.

وَجِاْیٓءَ یَوْمَىِٕذٍۭ بِجَهَنَّمَ ۚ یَوْمَىِٕذٍ یَتَذَكَّرُ ٱلْإِنسَٰنُ وَأَنَّىٰ
لَهُ ٱلذِّكْرَىٰ ﴿٢٣﴾ یَقُولُ یَٰلَیْتَنِی قَدَّمْتُ لِحَیَاتِی ﴿٢٤﴾ فَیَوْمَىِٕذٍ
لَّا یُعَذِّبُ عَذَابَهُۥٓ أَحَدٌ ﴿٢٥﴾ وَلَا یُوثِقُ وَثَاقَهُۥٓ أَحَدٌ ﴿٢٦﴾ یَٰٓأَیَّتُهَا
ٱلنَّفْسُ ٱلْمُطْمَىِٕنَّةُ ﴿٢٧﴾ ٱرْجِعِیٓ إِلَىٰ رَبِّكِ رَاضِیَةً مَّرْضِیَّةً ﴿٢٨﴾
فَٱدْخُلِی فِی عِبَٰدِی ﴿٢٩﴾ وَٱدْخُلِی جَنَّتِی ﴿٣٠﴾

سُورَةُ البَلَدِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِیمِ


لَآ أُقْسِمُ بِهَٰذَا ٱلْبَلَدِ ﴿١﴾ وَأَنتَ حِلٌّۢ بِهَٰذَا ٱلْبَلَدِ ﴿٢﴾ وَوَالِدٍ وَمَا وَلَدَ
﴿٣﴾ لَقَدْ خَلَقْنَا ٱلْإِنسَٰنَ فِی كَبَدٍ ﴿٤﴾ أَیَحْسَبُ أَن لَّن یَقْدِرَ عَلَیْهِ
أَحَدٌ ﴿٥﴾ یَقُولُ أَهْلَكْتُ مَالًا لُّبَدًا ﴿٦﴾ أَیَحْسَبُ أَن لَّمْ یَرَهُۥٓ أَحَدٌ
﴿٧﴾ أَلَمْ نَجْعَل لَّهُۥ عَیْنَیْنِ ﴿٨﴾ وَلِسَانًا وَشَفَتَیْنِ ﴿٩﴾ وَهَدَیْنَٰهُ
ٱلنَّجْدَیْنِ ﴿١٠﴾ فَلَا ٱقْتَحَمَ ٱلْعَقَبَةَ ﴿١١﴾ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا ٱلْعَقَبَةُ ﴿١٢﴾
فَكُّ رَقَبَةٍ ﴿١٣﴾ أَوْ إِطْعَٰمٌ فِی یَوْمٍ ذِی مَسْغَبَةٍ ﴿١٤﴾ یَتِیمًا ذَا مَقْرَبَةٍ
﴿١٥﴾ أَوْ مِسْكِینًا ذَا مَتْرَبَةٍ ﴿١٦﴾ ثُمَّ كَانَ مِنَ ٱلَّذِینَ ءَامَنُوا۟ وَتَوَاصَوْا۟
بِٱلصَّبْرِ وَتَوَاصَوْا۟ بِٱلْمَرْحَمَةِ ﴿١٧﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْمَیْمَنَةِ ﴿١٨﴾

(23) Aka kuma zo da Jahannama a wannan ranar. To fa a wannan ranar ne mutum zai tuna (sakacinsa), ta yaya wannan tunawar za ta yi masa amfani?
(24) Zai ce: "Kaitona, ina ma da na gabatar (da ayyukan alheri) a rayuwata!"
(25) To a wannan ranar ba wani daya da zai yi azaba irin azabarsa (watau Allah)
(26) Ba kuma ɗaya da zai yi ɗauri irin ɗaurinsa
(27) (Za a ce): Ya kai wannan rai mai nutsuwa
(28) Ka koma zuwa ga Ubangijinka kana mai yarda (da sakamako), abin yarda
(29) Don haka ka shiga cikin bayina
(30) Ka kuma shiga Aljannata

Sura Balad

(1) Na rantse da wannan gari (na Makka)
(2) Alhali kuwa kai an halatta maka wannan gari[1]
(3) (Na rantse) da mahaifi da abin da ya haifa[2]
(4) Haƙiƙa Mun halicci mutum cikin wahala
(5) Yanzu mutum yana tsammanin cewa wani ba zai sami iko a kansa ba?
(6) Yana cewa: "Na ɓatar da dukiya mai ɗimbin yawa."
(7) Shin yana tsammanin cewa ba wanda ya gan shi?
(8) Shin ba Mu sanya masa idanuwa biyu ba ne?
(9) Da harshe da kuma laɓɓa biyu?
(10) Muka kuma bayyana masa hanyoyi biyu[3]?
(11) Sai bai ƙetare hanya mai wahala[4] ba?
(12) Me kuma ya sanar da kai mece ce hanya mai wahala?
(13) (Watau) 'yanta wuyaye (bawa ko baiwa)
(14) Ko kuma ciyarwa a wata rana ta yunwa
(15) Ga maraya ma'abocin kusanci
(16) Ko miskini ma'abocin talauci
(17) Sannan kuma ya zama daga waɗanda suka yi imani, suka yi wa junansu wasiyya da yin haƙuri kuma suka yi wa juna wasiyya da tausayawa
(18) Waɗannan su ne ma'abota dama[5]

(1) Watau an halatta masa kashe wanda ya cancanci kisa a garin Makka. Ko kuma ana nufin Allah ya yi rantsuwa da Makka musamman lokacin da Annabi ( ) yake zaune a cikinta.
(2) Watau Annabi Adamu ( ) da zurriyarsa. Ko kuma duk wani mahaifi da duk wani wanda aka haifa.
(3) Watau hanyar alheri da hanyar sharri.
(4) Watau hanyar da ta raba tsakaninsa da gidan Aljanna.
(5) Watau 'yan Aljanna.


وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِنَا هُمۡ أَصۡحَٰبُ ٱلۡمَشۡـَٔمَةِ ١٩ عَلَيۡهِمۡ نَارٞ مُّؤۡصَدَةُۢ ٢٠

سُورَةُ الشَّمۡسِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلشَّمۡسِ وَضُحَىٰهَا ١ وَٱلۡقَمَرِ إِذَا تَلَىٰهَا ٢ وَٱلنَّهَارِ إِذَا جَلَّىٰهَا ٣ وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَغۡشَىٰهَا ٤ وَٱلسَّمَآءِ وَمَا بَنَىٰهَا ٥ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا طَحَىٰهَا ٦ وَنَفۡسٖ وَمَا سَوَّىٰهَا ٧ فَأَلۡهَمَهَا فُجُورَهَا وَتَقۡوَىٰهَا ٨ قَدۡ أَفۡلَحَ مَن زَكَّىٰهَا ٩ وَقَدۡ خَابَ مَن دَسَّىٰهَا ١٠ كَذَّبَتۡ ثَمُودُ بِطَغۡوَىٰهَآ ١١ إِذِ ٱنۢبَعَثَ أَشۡقَىٰهَا ١٢ فَقَالَ لَهُمۡ رَسُولُ ٱللَّهِ نَاقَةَ ٱللَّهِ وَسُقۡيَىٰهَا ١٣ فَكَذَّبُوهُ فَعَقَرُوهَا فَدَمۡدَمَ عَلَيۡهِمۡ رَبُّهُم بِذَنۢبِهِمۡ فَسَوَّىٰهَا ١٤ وَلَا يَخَافُ عُقۡبَٰهَا ١٥

سُورَةُ اللَّيۡلِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَغۡشَىٰ ١ وَٱلنَّهَارِ إِذَا تَجَلَّىٰ ٢ وَمَا خَلَقَ ٱلذَّكَرَ وَٱلۡأُنثَىٰٓ ٣ إِنَّ سَعۡيَكُمۡ لَشَتَّىٰ ٤ فَأَمَّا مَنۡ أَعۡطَىٰ وَٱتَّقَىٰ ٥ وَصَدَّقَ بِٱلۡحُسۡنَىٰ ٦ فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلۡيُسۡرَىٰ ٧ وَأَمَّا مَنۢ بَخِلَ وَٱسۡتَغۡنَىٰ ٨ وَكَذَّبَ بِٱلۡحُسۡنَىٰ ٩

(19) Waɗanda kuwa suka kafirce wa ayoyinmu, su ne ma'abota hagu[1] (20) A kansu akwai wuta abar kullewa

Sura Shams

(1) Na rantse da rana da walaharta (2) Da kuma wata idan ya bi ta (wato ranar)[2]
(3) Da kuma wuni idan ya bayyana ta (4) Da kuma dare idan ya lulluɓe ta (5) Da kuma sama da gininta (6) Da kuma ƙasa da shimfiɗarta (7) Da kuma rai da daidaitarsa
(8) Sai Ya kimsa masa (gane) lalacewarsa da taƙawarsa (9) Haƙiƙa wanda ya tsarkake shi (ran) ya rabauta (10) Haƙiƙa kuma wanda ya binne shi da saɓo ya taɓe
(11) Samudawa sun ƙaryata saboda ɗagawarsu (12) Yayin da mafi tsagerancinsu ya zabura (13) Sai Manzon Allah[3] ya ce da su: "Ku bar taguwar Allah da (ranar) shanta." (14) Sai suka ƙaryata shi sannan suka soke ta, sai Ubangijinsu Ya kama su da azaba saboda zunubinsu, sai Ya daidaita ta (watau ƙabilar wajen azaba) (15) Kuma ba Ya tsoron abin da zai biyo bayanta[4]

Sura Lail

(1) Na rantse da dare idan ya lulluɓe (da duhunsa)
(2) Da kuma wuni idan ya bayyana
(3) Da kuma halittar namiji da mace
(4) Lalle aikinku ya sha bamban
(5) To wanda ya ba da (haƙƙoƙin da ke kansa) ya kuma yi taƙawa
(6) Ya kuma gaskata (sakamako) mafi kyau
(7) To lalle ne za Mu sauƙaƙa masa (hanyar) Aljanna
(8) Amma kuma wanda ya yi rowa (da haƙƙin Allah) ya kuma wadatu (da neman lada)
(9) Kuma ya ƙaryata (sakamako) mafi kyau

(1) Watau 'yan wuta.
(2) Watau ya biyo bayan faxuwar rana.
(3) Watau Annabi Salihu ( ).
(4) Watau ba ya jin tsoron wani abu da hallaka su za ta haifar nan gaba.

فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلْعُسْرَىٰ ﴿١٠﴾ وَمَا يُغْنِى عَنْهُ مَالُهُۥٓ إِذَا تَرَدَّىٰٓ ﴿١١﴾ إِنَّ عَلَيْنَا
لَلْهُدَىٰ ﴿١٢﴾ وَإِنَّ لَنَا لَلْءَاخِرَةَ وَٱلْأُولَىٰ ﴿١٣﴾ فَأَنذَرْتُكُمْ نَارًا تَلَظَّىٰ ﴿١٤﴾
لَا يَصْلَىٰهَآ إِلَّا ٱلْأَشْقَى ﴿١٥﴾ ٱلَّذِى كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰ ﴿١٦﴾ وَسَيُجَنَّبُهَا
ٱلْأَتْقَى ﴿١٧﴾ ٱلَّذِى يُؤْتِى مَالَهُۥ يَتَزَكَّىٰ ﴿١٨﴾ وَمَا لِأَحَدٍ عِندَهُۥ مِن نِّعْمَةٍ
تُجْزَىٰٓ ﴿١٩﴾ إِلَّا ٱبْتِغَآءَ وَجْهِ رَبِّهِ ٱلْأَعْلَىٰ ﴿٢٠﴾ وَلَسَوْفَ يَرْضَىٰ ﴿٢١﴾

سُورَةُ الضُّحَىٰ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلضُّحَىٰ ﴿١﴾ وَٱلَّيْلِ إِذَا سَجَىٰ ﴿٢﴾ مَا وَدَّعَكَ رَبُّكَ وَمَا قَلَىٰ ﴿٣﴾
وَلَلْءَاخِرَةُ خَيْرٌ لَّكَ مِنَ ٱلْأُولَىٰ ﴿٤﴾ وَلَسَوْفَ يُعْطِيكَ رَبُّكَ
فَتَرْضَىٰٓ ﴿٥﴾ أَلَمْ يَجِدْكَ يَتِيمًا فَـَٔاوَىٰ ﴿٦﴾ وَوَجَدَكَ ضَآلًّا فَهَدَىٰ
﴿٧﴾ وَوَجَدَكَ عَآئِلًا فَأَغْنَىٰ ﴿٨﴾ فَأَمَّا ٱلْيَتِيمَ فَلَا تَقْهَرْ ﴿٩﴾
وَأَمَّا ٱلسَّآئِلَ فَلَا تَنْهَرْ ﴿١٠﴾ وَأَمَّا بِنِعْمَةِ رَبِّكَ فَحَدِّثْ ﴿١١﴾

سُورَةُ الشَّرْحِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

أَلَمْ نَشْرَحْ لَكَ صَدْرَكَ ﴿١﴾ وَوَضَعْنَا عَنكَ وِزْرَكَ ﴿٢﴾



(10) To lalle ne za Mu hore masa (hanyar) wuta
(11) Dukiyarsa kuma ba za ta amfane shi ba idan ya gangara (cikin wuta)
(12) Lalle bayyana hanyar shiriya a kanmu yake
(13) Kuma lalle lahira da duniya namu ne
(14) Don haka ina yi muku gargaɗin wata wuta mai ruruwa
(15) Ba mai shigar ta sai mafi tsiyacewa
(16) Wanda ya ƙaryata ya kuma ba da baya
(17) Kuma lalle za a nesantar da mafi taƙawa[1] daga gare ta
(18) Wanda yake ba da dukiyarsa yana neman tsarkaka
(19) Ba kuwa wani da ya yi masa wata ni'ima da za a saka masa (a kanta)[2]
(20) Sai dai don neman Fuskar Ubangijinsa Maɗaukaki
(21) Kuma lalle zai yarda (da sakamakon da za a ba shi)[3]

Sura Dhuha

(1) Na rantse da lokacin hantsi (2) Da kuma dare idan ya yi tsit[4]
(3) Ubangijinka bai bar ka ba, kuma bai ƙi ka ba (4) Kuma lalle lahira ta fi maka alheri a kan duniya (5) Kuma lalle Ubangijinka zai ba ka har sai ka yarda (da abin da Ya ba ka) (6) Shin bai same ka maraya ba sai Ya haɗa ka (da mai kula da kai)? (7) Ya kuma same ka marashin shiriya Ya shiryar (da kai)? (8) Ya kuma same ka matalauci Ya wadata (ka)? (9) Don haka maraya fa kada ka yi masa fin ƙarfi (10) Mai tambaya[5] kuma kada ka daka masa tsawa
(11) Amma kuma game da ni'imar Ubangijinka sai ka ba da labari

---

Sura Sharh

(1) Shin ba Mu yalwata maka ƙirjinka ba[6]?
(2) Muka kuma sauke maka nauye-nauyenka[7]?

---

(1) Da dama daga cikin malaman tafsiri sun bayyana cewa a nan ana nufin Abubakar As-Siddiq ( ).
(2) Watau ba yana ciyar da dukiyarsa ne don ya saka wa wani a kan wata ni'ima da ya yi masa ba.
(3) Watau gidan Aljanna a lahira.
(4) Watau ya lulluve komai da duhunsa, mutane su shiga mazaunansu don su yi barci.
(5) Watau mai neman taimako saboda buqata, ko mai tambaya don neman sani.
(6) Watau ya hore masa son sauraren wahayin da yake yiwo masa da kuma juriya a kan gallazawar mutanensa.
(7) Watau Allah ( ) ya gafarta masa duk wasu laifuka na baya da na nan gaba idan za su samu.



(3) Wanda ya nauyayi bayanka?
(4) Muka kuma ɗaukaka maka ambatonka[1]?
(5) To lalle tsanani yana tare da sauƙi
(6) Lalle tsananin yana tare da sauƙi
(7) Saboda haka idan ka gama (harkokinka) sai ka kafu (wajen bautar Allah)
(8) Sannan kuma ka yi kwaɗayi wajen Ubangijinka kawai


Sura Tin

(1) Na rantse da ɓaure da zaitun[2]
(2) Da (dutsen) Duri Sinina
(3) Da wannan garin amintacce (watau Makka)
(4) Haƙiƙa Mun halicci mutum a kan mafi kyan diri
(5) Sannan Muka mayar da shi mafi ƙasƙancin ƙasƙantattu[3]
(6) Sai fa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, to su kam suna da lada ba mai yankewa ba
(7) To (kai kafiri) me ya sa kake ƙaryata ranar sakamako bayan haka?
(8) Ashe Allah ba Shi ne Mafi iya hukuncin masu hukunci ba?

Sura Alaƙ

(1) Ka yi karatu da sunan Ubangijinka, Wanda Ya yi halitta
(2) Ya halicci mutum daga gudan jini[4]
(3) Ka yi karatu alhali Ubangijinka Shi ne mafi karamci
(4) Wanda Ya koyar ta (hanyar) alƙalami
(5) Ya koyar da mutum abin da bai sani ba
(6) Tabbas! Lalle (jinsin) mutum haƙiƙa yana yin ɗagawa
(7) Don ya ga kansa yana cikin wadata
(8) Lalle kuma zuwa ga Ubangijinka ne makomar (taka) take
(9) Ka ba ni labarin wanda yake hana
(10) Bawa yayin da ya yi salla
(11) Ka ba ni labari idan (shi Bawan) ya kasance a kan shiriya
(12) Ko kuma ya yi umarni da taƙawa

(1) Watau kamar ambatonsa a cikin kiran salla da iqama da tahiya da sauransu.
(2) Watau wuraren tsirowarsu, watau Sham, ko kuma su kansu waxanan bishiyoyin.
(3) Watau ya mayar da shi tsoho tukuf a duniya, ko kuma a lahira ya zamanto xan wuta.
(4) Watau bayan yana xigon maniyyi.


أَرَءَيْتَ إِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰٓ ﴿١٣﴾ أَلَمْ يَعْلَم بِأَنَّ ٱللَّهَ يَرَىٰ ﴿١٤﴾ كَلَّا لَئِن لَّمْ يَنتَهِ
لَنَسْفَعًۢا بِٱلنَّاصِيَةِ ﴿١٥﴾ نَاصِيَةٍ كَٰذِبَةٍ خَاطِئَةٍ ﴿١٦﴾ فَلْيَدْعُ نَادِيَهُۥ ﴿١٧﴾
سَنَدْعُ ٱلزَّبَانِيَةَ ﴿١٨﴾ كَلَّا لَا تُطِعْهُ وَٱسْجُدْ وَٱقْتَرِب ۩ ﴿١٩﴾

سُورَةُ القَدْرِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِنَّآ أَنزَلْنَٰهُ فِى لَيْلَةِ ٱلْقَدْرِ ﴿١﴾ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا لَيْلَةُ ٱلْقَدْرِ ﴿٢﴾
لَيْلَةُ ٱلْقَدْرِ خَيْرٌ مِّنْ أَلْفِ شَهْرٍ ﴿٣﴾ تَنَزَّلُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَٱلرُّوحُ فِيهَا
بِإِذْنِ رَبِّهِم مِّن كُلِّ أَمْرٍ ﴿٤﴾ سَلَٰمٌ هِىَ حَتَّىٰ مَطْلَعِ ٱلْفَجْرِ ﴿٥﴾

سُورَةُ البَيِّنَةِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

لَمْ يَكُنِ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ وَٱلْمُشْرِكِينَ مُنفَكِّينَ حَتَّىٰ
تَأْتِيَهُمُ ٱلْبَيِّنَةُ ﴿١﴾ رَسُولٌ مِّنَ ٱللَّهِ يَتْلُوا۟ صُحُفًا مُّطَهَّرَةً ﴿٢﴾ فِيهَا كُتُبٌ
قَيِّمَةٌ ﴿٣﴾ وَمَا تَفَرَّقَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَتْهُمُ
ٱلْبَيِّنَةُ ﴿٤﴾ وَمَآ أُمِرُوٓا۟ إِلَّا لِيَعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ
حُنَفَآءَ وَيُقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤْتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ ۚ وَذَٰلِكَ دِينُ ٱلْقَيِّمَةِ ﴿٥﴾

(13) Ka ba ni labari idan (shi mai hanawar) ya ƙaryata ya kuma ba da baya
(14) Shin bai sani ba cewa lalle Allah Yana ganin (sa)?
(15) A'aha! Tabbas idan bai hanu ba to za Mu ja shi ta makwarkwaɗar kai
(16) Makwarkwaɗar kai mai ƙaryatawa, mai aikata laifi
(17) To ya kirawo majalisar tasa
(18) Mu kuma lalle za Mu kirawo (mala'iku) zabaniyawa
(19) Faufau! Kada ka bi shi, ka kuma yi salla, ka kusanta (ga Allah)


Sura Kadar

(1) Lalle Mu Muka saukar da shi (Alƙur'ani) a daren Lailatul-Kadari[1] (dare mai daraja)
(2) Mene ne ya sanar da kai mece ce Lailatul-Kadari?
(3) (Daren) Lailatul-Kadari ya fi wata dubu alheri
(4) Mala'iku da Jibrilu suna ta saukowa da dukkanin al'amura a cikinsa da izinin Ubangijinsu
(5) Aminci ne shi (daren dukkansa) har zuwa hudowar alfijir

Sura Bayyina

(1) Waɗanda suka kafirta daga ma'abota littafi da mushirikai ba su zamanto masu barin abin da suke kai (na kafirci) ba har sai hujja bayyananniya ta zo musu
(2) (Watau) Manzo daga Allah da zai riƙa karanta (musu) takardu masu tsarki
(3) (Waɗanda) a cikinsu akwai hukunce-hukunce masu ƙima
(4) Waɗanda kuma aka bai wa littafi ba su rarraba ba[2] sai bayan da hujja bayyananniya ta zo musu
(5) Ba a kuma umarce su ba sai don su bauta wa Allah suna masu tsantsanta addini gare Shi, suna masu kauce wa ɓarna, suna kuma tsayar da salla, kuma suna ba da zakka. Wannan kuwa shi ne addinin miƙaƙƙiyar hanya

(1) Watau lokacin da aka fara saukar da jumullarsa a sama ta kusa, kamar yadda a cikin watan Ramadana ne ake fara saukar da shi ga Manzon Allah ( ) a kogon Hira.
(2) Watau Yahudawa da Nasara ba su rarrabu ba suka zama qungiya-qungiya wasu suka yi imani da Manzo Allah ( ), wasu kuma suka kafirce.


إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ وَٱلْمُشْرِكِينَ فِى نَارِ جَهَنَّمَ
خَٰلِدِينَ فِيهَآ أُوْلَٰٓئِكَ هُمْ شَرُّ ٱلْبَرِيَّةِ ۝٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمْ خَيْرُ ٱلْبَرِيَّةِ ۝٧ جَزَآؤُهُمْ
عِندَ رَبِّهِمْ جَنَّٰتُ عَدْنٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ
فِيهَآ أَبَدًا رَّضِىَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُواْ عَنْهُ ذَٰلِكَ لِمَنْ خَشِىَ رَبَّهُۥ ۝٨

سُورَةُ الزَّلْزَلَةِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِذَا زُلْزِلَتِ ٱلْأَرْضُ زِلْزَالَهَا ۝١ وَأَخْرَجَتِ ٱلْأَرْضُ أَثْقَالَهَا ۝٢ وَقَالَ
ٱلْإِنسَٰنُ مَا لَهَا ۝٣ يَوْمَئِذٍ تُحَدِّثُ أَخْبَارَهَا ۝٤ بِأَنَّ رَبَّكَ أَوْحَىٰ لَهَا
۝٥ يَوْمَئِذٍ يَصْدُرُ ٱلنَّاسُ أَشْتَاتًا لِّيُرَوْاْ أَعْمَٰلَهُمْ ۝٦ فَمَن يَعْمَلْ
مِثْقَالَ ذَرَّةٍ خَيْرًا يَرَهُۥ ۝٧ وَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ شَرًّا يَرَهُۥ ۝٨

سُورَةُ الْعَادِيَاتِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلْعَٰدِيَٰتِ ضَبْحًا ۝١ فَٱلْمُورِيَٰتِ قَدْحًا ۝٢ فَٱلْمُغِيرَٰتِ
صُبْحًا ۝٣ فَأَثَرْنَ بِهِۦ نَقْعًا ۝٤ فَوَسَطْنَ بِهِۦ جَمْعًا ۝٥

(6) Lalle wadanda suka kafirta daga ma'abota littafi da mushirikai suna cikin wutar Jahannama suna madawwama a cikinta. Wadannan su ne mafiya sharrin halitta
(7) Lalle wadanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, wadannan su ne mafiya alherin halitta
(8) Sakamakonsu a wajen Ubangijinsu gidajen Aljanna ne na dawwama wadanda koramu suke gudana ta karkashinsu suna madawwama a cikinsu har abada; Allah Ya yarda da su, su ma sun yarda da Shi. Wannan kuma (sakamako ne) ga wanda ya ji tsoron Ubangijinsa

Sura Zalzala

(1) Na rantse da (dawaki) masu sukuwa suna kukan ciki
(2) Sannan masu bugun kyastu da kofatai(3)
(3) Mutum kuma ya ce: "Me ya same ta?"
(4) A wannan ranar ne za ta ba da labaranta(2)
(5) Don Ubangijinka Ya umarce ta (da yin haka)
(6) A wannan ranar mutane za su fito a warwatse, don a nuna musu ayyukansu
(7) To duk wanda ya yi aikin alheri daidai da zarra zai gan shi
(8) Wanda kuma duk ya yi aikin sharri daidai da zarra zai gan shi


Sura Adiyat

(1) Pelos cabalos de batalha, ofegantes (kuando em combate),
(2) Kue soltam faíscas (ao bater os seus cascos contra as pedras),
(3) Sannan masu kai hari da asuba
(4) Sai suka tayar da kura da ita (sukawar tasu)
(5) Sai kuma suka shiga tsakiyar taro (da mahayansu)

(1) Watau ta fitar da mutanen da ke cikinta da sauran ma'adanan qarqashinta.

(2) Watau ayyukan da aka yi a kanta masu kyau da munana.

(3) Watau suna qyasta wuta da kofatansu idan suka daki duwatsu da su.


إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لِرَبِّهِۦ لَكَنُودٌ ﴿٦﴾ وَإِنَّهُۥ عَلَىٰ ذَٰلِكَ لَشَهِيدٌ ﴿٧﴾ وَإِنَّهُۥ لِحُبِّ
ٱلْخَيْرِ لَشَدِيدٌ ﴿٨﴾ أَفَلَا يَعْلَمُ إِذَا بُعْثِرَ مَا فِى ٱلْقُبُورِ ﴿٩﴾
وَحُصِّلَ مَا فِى ٱلصُّدُورِ ﴿١٠﴾ إِنَّ رَبَّهُم بِهِمْ يَوْمَئِذٍ لَّخَبِيرٌۢ ﴿١١﴾

سُورَةُ القَارِعَة

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلْقَارِعَةُ ﴿١﴾ مَا ٱلْقَارِعَةُ ﴿٢﴾ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا ٱلْقَارِعَةُ ﴿٣﴾ يَوْمَ
يَكُونُ ٱلنَّاسُ كَٱلْفَرَاشِ ٱلْمَبْثُوثِ ﴿٤﴾ وَتَكُونُ ٱلْجِبَالُ
كَٱلْعِهْنِ ٱلْمَنفُوشِ ﴿٥﴾ فَأَمَّا مَن ثَقُلَتْ مَوَٰزِينُهُۥ ﴿٦﴾ فَهُوَ فِى
عِيشَةٍ رَّاضِيَةٍ ﴿٧﴾ وَأَمَّا مَنْ خَفَّتْ مَوَٰزِينُهُۥ ﴿٨﴾ فَأُمُّهُۥ هَاوِيَةٌ
﴿٩﴾ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا هِيَهْ ﴿١٠﴾ نَارٌ حَامِيَةٌۢ ﴿١١﴾

سُورَةُ التَّكَاثُر

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

أَلْهَىٰكُمُ ٱلتَّكَاثُرُ ﴿١﴾ حَتَّىٰ زُرْتُمُ ٱلْمَقَابِرَ ﴿٢﴾ كَلَّا سَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿٣﴾ ثُمَّ
كَلَّا سَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿٤﴾ كَلَّا لَوْ تَعْلَمُونَ عِلْمَ ٱلْيَقِينِ ﴿٥﴾ لَتَرَوُنَّ ٱلْجَحِيمَ ﴿٦﴾
ثُمَّ لَتَرَوُنَّهَا عَيْنَ ٱلْيَقِينِ ﴿٧﴾ ثُمَّ لَتُسْـَٔلُنَّ يَوْمَئِذٍ عَنِ ٱلنَّعِيمِ ﴿٨﴾

(6) Lalle mutum tabbas mai yawan butulci ne ga Ubangijinsa
(7) Lalle kuma shi shaida ne a kan haka
(8) Lalle shi kuma mai tsananin son alheri ne[1]
(9) Shin bai sani ba ne idan aka bankaɗo abubuwan da suke cikin ƙaburbura?
(10) Aka kuma tattaro abubuwan da suke cikin ƙiraza?
(11) Lalle a wannan ranar tabbas Ubangijinsu Masani ne game da su

Sura Kari'a

(1) Mai ƙwanƙwasa (zukata da tsoro)
(2) Mece ce mai ƙwanƙwsa (zukata da tsoro)?
(3) Kuma me ya sanar da kai mece ce mai ƙwanƙwasa (zukata da tsoro)?
(4) (Ita ce) ranar da mutane za su zama kamar ɗangon fari masu bazuwa
(5) Duwatsu kuma su zama kamar kaɗaɗɗiyar auduga[2]
(6) To amma wanda ma'aunan ayyukansa suka yi nauyi
(7) To shi kam yana cikin rayuwa mai gamsarwa
(8) Amma kuma duk wanda ma'aunan ayyukansa suka yi shafal
(9) To shi makomarsa (wutar) Hawiya ce
(10) Kuma me ya sanar da kai mece ce ita?
(11) Wuta ce mai tsananin zafi

Sura Takasur

(1) Alfahari da yawan ('ya'ya da dukiya) ya shagaltar da ku[3]
(2) Har kuka (mutu kuka) ziyarci ƙaburbura
(3) A'aha! (haka bai kamace ku ba) da sannu za ku sani
(4) Sannan a'aha, da sannu za ku sani
(5) Tabbas da za ku yi sani, sani na sakankancewa[4]
(6) Tabbas haƙiƙa za ku ga wutar Jahimu
(7) Sannan tabbas haƙiƙa za ku gan ta gani da ido na sakankancewa
(8) Sannan kuma tabbas lalle za a tambaye ku a wannan ranar game da ni'imomin (da kuka mora a duniya)

(1) Watau yana da tsananin son dukiya, wannan ne kuma yake sanya shi rowa.
(2) Watau saboda rashin nauyinsu da warwatsuwarsu a cikin sararin sama.
(3) Watau su xauke musu hankali har su kai ga barin xa'ar Allah.
(4) Watau wanda babu kokwanto ko kaxan a cikinsa.



Sura Asr

(1) Na rantse da zamani[1]
(2) Lalle mutum yana cikin asara
(3) Sai dai waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, suka kuma yi wa juna wasiyya da gaskiya, suka kuma yi wa juna wasiyya da haƙuri

Sura Humaza

(1) Tsananin azaba ya tabbata ga duk wani mai yawan ƙyafice mai yawan suka[2]
(2) Wanda ya tara dukiya ya ƙididdige ta
(3) Yana zaton cewa dukiyarsa za ta dawwamar da shi
(4) Faufau! Tabbas lalle sai an jefa shi cikin (wutar) 'Huɗama'[3]
(5) Me kuma ya sanar da kai irin girman 'Huɗama'?
(6) Wuta ce ta Allah abar hurawa
(7) Wadda take mamaye zukata
(8) Lalle ita abar kullewa ce da su[4]
(9) A cikin ginshiƙai miƙaƙƙu (da suka kewaye ta)

Sura Fil

(1) Shin ba ka ga yadda Ubangijinka Ya yi wa ma'abota giwa[5] ba?
(2) Ashe bai mayar da makircinsu cikin watsewa ba?
(3) Ya kuma aiko musu da tsuntsaye dodo-dodo?
(4) Suna jifan su da duwatsu na ƙonanniyar laka?
(5) Sai da Ya mayar da su kamar karmami da aka cinye[6]?

سُورَةُ العَصۡرِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلۡعَصۡرِ ﴿١﴾ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَفِي خُسۡرٍ ﴿٢﴾ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلۡحَقِّ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلصَّبۡرِ ﴿٣﴾

سُورَةُ الهُمَزَةِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَيۡلٞ لِّكُلِّ هُمَزَةٖ لُّمَزَةٍ ﴿١﴾ ٱلَّذِي جَمَعَ مَالٗا وَعَدَّدَهُۥ ﴿٢﴾ يَحۡسَبُ أَنَّ مَالَهُۥٓ أَخۡلَدَهُۥ ﴿٣﴾ كَلَّاۖ لَيُنۢبَذَنَّ فِي ٱلۡحُطَمَةِ ﴿٤﴾ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡحُطَمَةُ ﴿٥﴾ نَارُ ٱللَّهِ ٱلۡمُوقَدَةُ ﴿٦﴾ ٱلَّتِي تَطَّلِعُ عَلَى ٱلۡأَفۡـِٔدَةِ ﴿٧﴾ إِنَّهَا عَلَيۡهِم مُّؤۡصَدَةٞ ﴿٨﴾ فِي عَمَدٖ مُّمَدَّدَۭ ﴿٩﴾

سُورَةُ الفِيلِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

أَلَمۡ تَرَ كَيۡفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِأَصۡحَٰبِ ٱلۡفِيلِ ﴿١﴾ أَلَمۡ يَجۡعَلۡ كَيۡدَهُمۡ فِي تَضۡلِيلٖ ﴿٢﴾ وَأَرۡسَلَ عَلَيۡهِمۡ طَيۡرًا أَبَابِيلَ ﴿٣﴾ تَرۡمِيهِم بِحِجَارَةٖ مِّن سِجِّيلٖ ﴿٤﴾ فَجَعَلَهُمۡ كَعَصۡفٖ مَّأۡكُولِۢ ﴿٥﴾

(1) Wannan ya qunshi dare da rana waxanda su ne mahallin dukkan ayyukan bayi.
(2) Watau yawan qyafice ga mutane, yana kuma yawan sukan su da aibata su a bayan idanuwansu..
(3) Ita ce wuta mai kakkarya duk wani abu da aka jefa cikinta saboda tsananin zafinta da azabarta.
(4) Watau za a kulle kafirai a cikin ruf babu fita.
(5) Watau runduna ce ta mayaqa daga qasar Yaman qarqashin jagorancin Abrahata, suka nufo Makka da niyyar rushe Xakin Ka'aba. A tare da su akwai wata babbar giwa. Allah ya hallaka su baki xaya..
(6) Wannan babban abu ya auku ne a shekara ta 571 bayan haihuwar Annabi Isa ( ). A shekarar ne aka haifi Manzon Allah ( ).



Sura Kuraish

(1) Domin sabon da Kuraishawa suka yi
(2) Sabonsu na yin safara a lokacin ɗari (zuwa ƙasar Yaman) da lokacin bazara (zuwan ƙasar Sham)[1]
(3) To sai su bauta wa Ubangijin wannan Ɗakin[2]
(4) Wanda Ya ciyar da su daga yunwa, Ya kuma amintar da su daga tsoro

سُورَةُ قُرَيْشٍ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

لِإِيلَٰفِ قُرَيْشٍ ﴿١﴾ إِۦلَٰفِهِمْ رِحْلَةَ ٱلشِّتَآءِ وَٱلصَّيْفِ
﴿٢﴾ فَلْيَعْبُدُوا۟ رَبَّ هَٰذَا ٱلْبَيْتِ ﴿٣﴾ ٱلَّذِىٓ أَطْعَمَهُم
مِّن جُوعٍ وَءَامَنَهُم مِّنْ خَوْفٍۭ ﴿٤﴾

سُورَةُ الْمَاعُونِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

أَرَءَيْتَ ٱلَّذِى يُكَذِّبُ بِٱلدِّينِ ﴿١﴾ فَذَٰلِكَ ٱلَّذِى يَدُعُّ
ٱلْيَتِيمَ ﴿٢﴾ وَلَا يَحُضُّ عَلَىٰ طَعَامِ ٱلْمِسْكِينِ ﴿٣﴾ فَوَيْلٌ
لِّلْمُصَلِّينَ ﴿٤﴾ ٱلَّذِينَ هُمْ عَن صَلَاتِهِمْ سَاهُونَ
﴿٥﴾ ٱلَّذِينَ هُمْ يُرَآءُونَ ﴿٦﴾ وَيَمْنَعُونَ ٱلْمَاعُونَ ﴿٧﴾

سُورَةُ الْكَوْثَرِ

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِنَّآ أَعْطَيْنَٰكَ ٱلْكَوْثَرَ ﴿١﴾ فَصَلِّ لِرَبِّكَ وَٱنْحَرْ ﴿٢﴾
إِنَّ شَانِئَكَ هُوَ ٱلْأَبْتَرُ ﴿٣﴾

Sura Ma’un

(1) Shin ka ga wanda yake ƙaryata ranar sakamako?
(2) To shi ne wanda yake ingije maraya (daga haƙƙinsa)
(3) Ba kuma ya kwaɗaitarwa wajen ciyar da miskini
(4) To tsananin azaba ya tabbata ga masallata
(5) Waɗanda suke masu rafkana su bar sallarsu[3]
(6) Waɗanda su ne suke yin riya
(7) Suke kuma hana kayan taimako[4]

Sura Kausar

(1) Lalle Mu Mun ba ka alheri mai yawa[5]
(2) To sai ka yi salla don Ubangijinka, ka kuma soke (abin hadayarka)
(3) Lalle mai ƙin ka shi ne mai yankakken alheri[7]

(1) A cikin aminci ba tare da tsoron komai ba.

(2) Watau Xakin Ka’aba mai alfarma.

(3) Watau ba sa yin ta a kan lokaci, ko ma su bar sallar a wasu lokuta ba tare da sun yi ta ba.

(4) Watau ba sa bayar da zakkar dukiyoyinsu, ba sa taimaka wa masu buqata, ko kayan aro ba sa bayarwa.

(5) Watau qoramar Alkausara ta gidan Aljanna.

(6) Watau wanda a duk sanda aka tuna da shi za a yi tir da shi.



Sura Kafirun

(1) Ka ce: “Ya ku waɗannan kafirai
(2) “Ba zan bauta wa abin da kuke bauta wa ba
(3) “Ku kuma ba masu bautar abin da nake bauta wa ba ne
(4) “Ni kuma ba mai bauta wa abin da kuka bauta wa ba ne
(5) “Ku ma ba za ku bauta wa abin da nake bauta wa ba
(6) “Addininku na gare ku, ni ma kuma addinina na gare ni[1].”

سُورَةُ الكَافِرُونَ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

قُلْ يَا أَيُّهَا الْكَافِرُونَ ﴿١﴾ لَا أَعْبُدُ مَا تَعْبُدُونَ ﴿٢﴾
وَلَا أَنتُمْ عَابِدُونَ مَا أَعْبُدُ ﴿٣﴾ وَلَا أَنَا عَابِدٌ مَّا عَبَدتُّمْ ﴿٤﴾
وَلَا أَنتُمْ عَابِدُونَ مَا أَعْبُدُ ﴿٥﴾ لَكُمْ دِينُكُمْ وَلِيَ دِينِ ﴿٦﴾

Sura Nasr

(1) Idan nasarar Allah ta zo da kuma buɗe (Makka)
(2) Ka kuma ga mutane suna shiga addinin Allah ƙungiya-ƙungiya
(3) To ka yi tasbihi da yabon Ubangijinka, ka kuma nemi gafararsa. Lalle Shi Ya kasance Mai karɓar tuba ne

سُورَةُ النَّصْرِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

إِذَا جَاءَ نَصْرُ اللَّهِ وَالْفَتْحُ ﴿١﴾ وَرَأَيْتَ النَّاسَ
يَدْخُلُونَ فِي دِينِ اللَّهِ أَفْوَاجًا ﴿٢﴾ فَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ
وَاسْتَغْفِرْهُ إِنَّهُ كَانَ تَوَّابًا ﴿٣﴾

Sura Masad

(1) Hannayen Abu Lahabi[2] sun halaka, shi ma kuma ya halaka
(2) Dukiyarsa da abin da ya tsuwurwurta ba su amfana masa komai ba
(3) Ba da daɗewa ba zai shiga wuta mai balbali
(4) Da kuma matarsa mai yawan ɗaukar kayan ƙaya[3]
(5) A wuyanta akwai igiyar kaba mai ingantacciyar tukka. (a ranar alƙiyama)

سُورَةُ المَسَدِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ


تَبَّتْ يَدَا أَبِي لَهَبٍ وَتَبَّ ﴿١﴾ مَا أَغْنَىٰ عَنْهُ مَالُهُ وَمَا كَسَبَ ﴿٢﴾
سَيَصْلَىٰ نَارًا ذَاتَ لَهَبٍ ﴿٣﴾ وَامْرَأَتُهُ حَمَّالَةَ الْحَطَبِ ﴿٤﴾
فِي جِيدِهَا حَبْلٌ مِّن مَّسَدٍ ﴿٥﴾

---

(1) Annabi ( ) ya ga wani yana karanta wannan Surar sai ya ce: “Amma dai wannan haqiqa ya kuvuta daga shirka”.

(2) Abu Lahab, xaya ne daga baffannin Manzon Allah wanda ya nuna wa Annabi ( ) qiyayya ya mutu yana kafiri.

(3) Watau Ummu Jamil, ta kasance tana zuba wa Annabi ( ) qaya a kan hanyarsa domin ya taka.


سُورَةُ الإِخلَاصِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قُلۡ هُوَ ٱللَّهُ أَحَدٌ ﴿١﴾ ٱللَّهُ ٱلصَّمَدُ ﴿٢﴾ لَمۡ يَلِدۡ وَلَمۡ يُولَدۡ ﴿٣﴾
وَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ كُفُوًا أَحَدُۢ ﴿٤﴾

سُورَةُ الفَلَقِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قُلۡ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلۡفَلَقِ ﴿١﴾ مِن شَرِّ مَا خَلَقَ ﴿٢﴾ وَمِن شَرِّ
غَاسِقٍ إِذَا وَقَبَ ﴿٣﴾ وَمِن شَرِّ ٱلنَّفَّٰثَٰتِ فِي ٱلۡعُقَدِ ﴿٤﴾
وَمِن شَرِّ حَاسِدٍ إِذَا حَسَدَ ﴿٥﴾

سُورَةُ النَّاسِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قُلۡ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلنَّاسِ ﴿١﴾ مَلِكِ ٱلنَّاسِ ﴿٢﴾ إِلَٰهِ
ٱلنَّاسِ ﴿٣﴾ مِن شَرِّ ٱلۡوَسۡوَاسِ ٱلۡخَنَّاسِ ﴿٤﴾ ٱلَّذِي
يُوَسۡوِسُ فِي صُدُورِ ٱلنَّاسِ ﴿٥﴾
مِنَ ٱلۡجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ ﴿٦﴾

Sura Ikhlas

(1) Ka ce: “Shi Allah Daya ne[1]
(2) “Allah Abin nufa da bukatu[2]
(3) “Bai haifa ba, kuma ba a haife Shi ba
(4) “Kuma babu wani da ya kasance kini a gare Shi[3].”

Sura Falak

(1) Ka ce: “Ina neman tsari da Ubangijin asuba
(2) “Daga sharrin abin da Ya halitta[4]
(3) “Da kuma sharrin dare idan ya lulluɓe da duhu
(4) “Da kuma sharrin mata masu tofi a cikin kulle-kulle
(5) “Da kuma sharrin mai hassada yayin da ya yi hassadar.”

Sura Nas

(1) Ka ce: “Ina neman tsari da Ubangijin mutane
(2) “Sarkin mutane
(3) “Abin bautar mutane
(4) “Daga sharrin mai sa waswasi[5], mai nokewa[6]
(5) “Wanda yake yin waswasi a cikin kirazan mutane
(6) “Daga aljannu da na mutane[7].”

(1) Watau a Zatinsa da siffofinsa da ayyukansa, kuma shi kaxai ya cancanci a bauta masa.

(2) Watau wanda shugabanci ya tuqe zuwa gare shi, domin ya tattara dukkan siffofin kamala da xaukaka.

(3) Domin babu mai kama da shi a sunayensa da siffofinsa da ayyukansa.

(4) Watau duk wani mahluqi mai cutarwa, mutum ne ko aljani ko dabba.

(5) Watau kowane shaixani.

(6) Watau duk sanda xan’adam ya ambaci Allah.1- Watau shi wannan shaixani ana samun sa cikin mutane da aljanu.